TARIHIN GARIN KADUNA
HEDKWATAR JIHAR AREWA

YUSUFU NADABO

Haqin Mallaka © Dr. Yusufu Nadabo Abdullahi

An fara bugawa a 1988
An sake bugawa da faxaxawa a 2010

ISBN: 978 – 2368 – 35 – 0

Zanen *Cartoon*:
Mu'azu Sani Muhammad

Bugawa:
Kamfanin Xab'i na Jami'ar Ahmadu Bello,
Jakar Gidan Waya 1094, Samaru, Zaria, Nijeriya.
Tarho: 069-550054, 08065949711

Na wallafa wannan littafi ne domin tunawa da Kakana Sarkin Alaro Malam Isa da leburorin da suka shimfixa hanyar jirgin qasa daga garin Baro zuwa birnin Kano a shekarar 1907 zuwa 1911.

GABATARWA

Ba shakka Dr. Yusufu Nadabo, ko da shike shi likita ne na mutane, amma duk da haka ya kasance yana da matuqar sha'awa a fannin tarihi har ya yi qoqari ya rubuta wannan tarihi a kan garin Kaduna. Duk mai sha'awar ya san abin da ya auku baya, kafin wannan gari ya zo ya zama yadda yake a yanzu, ba shakka idan ya karanta wannan littafi zai sami cikakken bayani game da shi.

Masana tarihi a qasar nan ta Nijeriya, sun yi ta rubuce-rubuce a kan mutane da halin zamansu, a kan garuruwa da yadda suka faro. Daxaxxun garuruwa irin su Zariya da Kano da Katsina da Rano da Birnin Kebbi a misali, sun fi samun a rubuta wani abu game da su a tarihi. Saboda mafi yawan tarihin da muke da shi, ya soma ne a daxaxxun garuruwa ko kusa da su. Sai ya kasance garuruwa waxanda aka kafa a cikin wannan qarni na Ashirin ba a cika rubuta wani abu na tarihi a kansu ba. Dalili shi ne, wataqila ba a xauka cewa abin da ke faruwa a waxannan wurare tarihi ne ba. Kaduna tana cikin irin waxannan garuruwa. Har yanzun nan za a sami tsofaffi masu rai waxanda za su iya ba da cikkaken labarin yadda Kaduna ta soma tun da aka baro aka mayar da Kaduna ta zama hedkwatar Arewa baki xaya.

Irin waxannan dattijai masana tarihi, kullum raguwa suke yi, ba zai zama abin mamaki ba, idan wata rana mun wayi gari mun rasa waxanda aka yi wannan faman da su.

Saboda haka aiki irin wannan da Dr. Yusufu Nadabo ya yi ya zama muhimmi a gare mu. Yanzu muna da komai a tsare don na baya su masu karanta su ga yadda aka faro, a cikin wannan littafi na tarihin garin Kaduna.

Abin da Dr. Yusufu Nadabo ya rubuta zai yi amfani matuqa a wajen xalibai masu binciken tarihi da kuma hukuma, don ta qara gane mutanenta da bambance-bambancen da ke tsa kanin su.

Su kuma mutane idan suka yi amfani da irin wannan bayani da ke qunshe a cikin wannan littafi, za su gane matsayinsu a wannan birni na Kaduna kuma zai rage husuma da zargin juna da ake yi lokaci-lokaci.

Na shawarci duk wani mai sha'awar tarihin qasar nan ya nemi wannan littafi ya karanta. Ba shakka zai qaru da shi kuma zai fahimci abin da nike faxa a nan.

MUHAMMADU BACHAKA
Argungu

SANYA ALBARKA

Tarihin gari, labarin mutannen da suka kafa wannan gari ne da kuma waxanda suka zo suka havaka shi. Sai wannan littafi ya zama tarihin muhimman mutanen da suka taso daga Dungurun (Zungeru) suka tare a garin Kaduna, a matsayinta na Hedkwatar Arewa. Saboda haka ne ya qunshi labaran vangarorin jama'a waxanda suka haxa da Turawan Mulki, da Sarakuna, da Sojoji, da leburori, da Ma'aikata da 'Yan siyasa, Attajirai da malaman Qabilu daban-daban da kuma mabiya addinai da suka bambanta da juna. A wannan littafi an yi qoqari mutuqar gaske wajen baiwa kowane vangare haqqinsa wajen bayar da gudunmawar da ya bayar wajen ciyar da wannan gari gaba tare da kyautata jin daxin jama'a.

Kamar yadda Arewa take jiha mai bambanci da ban mamaki, haka garin Kaduna hedkwatarta yake. Wannan gari ya taso cikin sa'a, don haka ya bunqasa cikin hanzari har ya zama wani irin gari qi-faxi ba a Nijeriya kawai ba har ma a nahiyar Afirka baki xaya. Saboda wannan gari ya kafu da kyakkyawan harsashin da *Lord Frederick Lugard* ya kafa, wanda shi ne Gwamna na Farko na jihar Arewa da kuma Firimiyan Arewa Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato, wanda shi ne ya bunqasa shi har ya dace da hedkwatar wannan qasaitacciyar Jiha. Haka kuma Gwamnoni a lokuta daban-daban sun bi sawu wajen wannan aiki.

Haka kuma tarihin gari, labarin xaixaikun mutane ne waxanda suka bayar da gudunmawoyi iri-iri wajen bunqasa ci gaban wannan gari. A wajen bada waxannan labarai an fi raja'a ne a kan tituna da gine-ginen gidaje da kamfanonin da suka kafa a fafitikarsu ta havaka garin. Amma a wannan hali ba safai ake bayar da gudunmawoyi da Sarakunan Arewa suka baiwa Jihar Arewa ba tun daga shigowar Turawan Mulki, a lokacin da suka angije Daular Usumaniyya a shekarar 1903 har ya zuwa shekarar 1966, lokacin da sojoji suka hanvare Siyasar Farko, a wani mummunan jiyun Mulki. Abin sha'awa ne da wannan littafi ya haskaka irin taka rawar-gani da Sarakuna da Shugabannin Jihar Arewa suka yi a cikin waxannan shekaru sittin da uku wajen ciyar da da garin Kaduna gaba da kuma Jihar Arewa baki xaya.

Har ila yau a wajen bayar da tarihin al'ummomin da suka gabata, wannan littafi bai tsaya a kan wahalhalu da nasarorin da suka samu ba, sai da ya kawo irin zama na gasa da hamayya da suka wa kana a tsa kanin jihohin nan uku – Jihar Arewa, Jihar Yamma da Jihar Gabas a lokacin fafitikar kafa sabuwar Nijeriya. Bugu da qari yana da amfani saboda fahimtar irin zaman da aka yi jiya zai

taimaka wajen kyautata zaman mu a yau, zai kuma taimaka wajen yi wa gobe kyakkyawan tanadi. Saboda haka ne ya zama wajibi mu kare addininmu, da gidajen Sarakuna da masarautunsu da kyawawan xabiu da al'adunmu; mu kuma haxe su don su tafi daidai da zamani. Wannan littafi ya tunatar da mu aqidar da Firimiya Sir Ahmadu Bello ya dasa a Arewa, wadda itace Aiki da Ibada, don haka sai ya zama wajibi mu raya wannan aqidar kuma taken Jihar Arewa na asali, mu kuma aiwatar da shi domin samun ci gaba. Dalili kuwa shi ne, sirrin bunqasa da buwayar Jihar Arewa sun ta'allaqa ne a kan addini da al'adun jama'arta, saboda haka kada mu bari su zaizaye da sunan ci gaban zamani.

Haka kuma wannan littafi na xauke ne da tarihin muhimman mutane waxanda suka zama ababen misali a harkokin rayuwar jama'a daga kowane sashe na wannan jihar. A kuma fafitikarsu ta gina sabuwar Arewa, sun fuskanci qalubale iri-iri, sun yi qurarai sun kuma samu nasarori a harkoki da yawa. Saboda haka wajibi ne mu yi nazarin wancan zamani sosai domin mu samu darussan da za su taimake mu wajen fuskantar namu qalubalen a wannan zamani. Saboda masu hikima sun ce, "idan mutum yana son ya san kansa, to, ya karanci tarihin iyayensa." Ya kamata mu 'yan Arewa mu san kanmu domin mu riqa yin abubuwan da suka kamace mu. Domin yin haka zai taimake mu wajen fahintar rikita-rikitar wannan zamani da kuma zamantakewar mu da mutanen Kudu. Ya zama wajibi mu yi zaman tarayya a wannan qasa amma ba tarayya a al'adu da xabi'u ba. Don ya kamata kowane tsuntsu ya riqa kukan gidansu. Saboda yin haka ne zai taimake mu gaya wajen mutunta al'adu da jure halaye da xabi'un qabilu daban don samun sahalewa wajen zamantakewar jama'a. garin Kaduna ya nuna misali mai lyau wajen zamantakewar qabilu iri-iri cikin zaman lafiya da lumana.

Abin sha'awa shi ne yadda littafin ya yi bayani a kan Siyasa da Sarakuna da kuma yadda wannan shiri ya taimaka ma Siyasar Farko ya kuma ciyar da wannnan Jiha gaba. Na yi imani a yanzu ma shigar da Sarakuna cikin Siyasa ka'in da na'in zai taimaka matuqar gaske wajen maida Arewa sahun gaba a harkokin ci gaban xan-Adam da kuma fuskantar qalubalen wannan Zamani. Kowace qasa na yi wa Dimukuraxiyya gyaran fuska ta yadda zata dace da addini da xabi'unta domin samun ci gaban jama'arta da kyauta rayuwarsu.

Littafin ya jawo hankalimmu wajen suna da 'yan Arewa suka yi wajen aminci, da adalci da jarunta da sauran halayen qwarai, waxanda suka zama ababen nuna misali a wannan zamani. Tun fil azal aikin Tsaro (na Soja da 'Yan Sanda) wani fanni ne da 'yan Arewa suka yi suna domin sun nuna hikima da jarunta a lokacin

yaqin Duniya na Xaya da na Biyu, wasu halaye ne da suka baiwa Arewa suna ba ga Qasar Ingila ba har ma a duniya baki xaya. A wancan lokacin, aikin Tsaro na 'yan Arewa ne muxlaqan wanda ta haka ne Arewa ta samu karvuwa ta musamman ga Qasar Ingila da kuma Qasashen mulkinta wato *Commonwealth of Nations*. Anan ma Sarakuna ne suka taimaka wajen kafa kyakkyawan harsashin aikin soja a Arewa, wanda ya yi tasiri mai kyau ba a Jihar Arewa ba har ma da gidajen Sarakunan kansu. A zamanimmu a yau, Sarakuna da yawa a Arewa sun yi aikin Soja.

Daga qarshe, ina rokon Allah Ya albarkaci wannan littafi, ina kuma kira ga kowane mutum ya karanta shi domin zai fahimci garin Kaduna da wasu labarai na Jihar Arewa kamar yadda ya kamata. Ina kuma fatan wannan littafi zai zaburar da matasa domin su yi bincike zurfafa a kan batutuwan da littafin ya tavo. Wannan zamani ne na karatu da bincike, da rubuce-rubuce saboda haka bai kamata abar samari da 'yan matanmu a baya ba. Na yi imani, irin wannan aiki zai zaburar da su wajen fuskantar wannan qalubale. Hasali ma dai, ci gaban wannan jiha a fannin Ilimi ya dogara ne ga hukuma da attajirai da jama'ar Arewa baki xaya, saboda kowa na da gudunmawar da zai bayar wajen farfaxo da Ilimi, ta hanyar karatu da rubuce-rubuce masu amfani.

Hon. Justrice Umar Abdullahi (Rtd), CON, *Walin Hausa,*
Tsohon Shugaban Kotun Xaukaka Qara Ta Nijeriya
Almuharram 1431 AH/17th December, 2009

MATASHIYA

Alhaji Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato, bai qawata garin Kaduna da gine-gine ba, sai da ya yi wa garin kyakkyawar fahimta ta tarihi, ya kuma hangi tasirin wannan gari a Nijeriya. Saboda shi mutum ne wanda ba ya shiga al'amari, sai ya karanci al'amarin da idon basira. Saboda Kaduna gari ne da zai iya kawo riginginmu a tsa kanin qabilu mazauna cikinsa, ko kuma a samu taqaddama da masarautar Zazzau, wajen tafiyar da mulkin wannan gari mai albarka. Waxannan dalilai sun tilasta a fahimci tarihin wannan gari sosai, saboda gudun kada a yi kitso da kwarkwata. Firimiya ya ba da taqaitaccen tarihin garin Kaduna da kuma matsalolin da garin ke fuskanta a littafinsa *Rayuwata,* wanda ya zama matashiya ne ga fahimtar wannan aiki. Sir Ahmadu Bello ya ce:

"An yi shekaru da dama, maganar yadda za a mallaki Kaduna tana ta bai wa Turawan Ingilishi na Mulki wahala a zukatansu. Kaduna dai bariki ce. Cikin 1913 duk karkarar hedkwatar nan tamu, da mu ke ciki, kusan a ce babu kowa a lokacin. Akwai 'yan qauyukan Gwari a warwatse jefi-jefi. In ma ba don hanyar jirgin da ta taso daga Ikko ta ratsa wurin ta wuce Kano ba, da sai a ce babu abin da ya haxa su da junansu. Suna cikin yankin qasar Zazzau ne, wadda take xaya ce daga cikin Hausa Bakwai na asali. Qasar ta yi kudu har wajen mil xari, wajen gabas kuma sai da ta dangana da manyan duwatsun nan na Qasar Kuza. A nan ne ma Sarakunan Zazzau na da suke kawo hari, su yi ta kama bayi. Har yanzu kuwa a qarqashin Zazzau wurin yake.

"Hanyar jirgi ta qetare Kogin Kaduna, da aka yi masa wata gada mai tsawo kafa xari shida. In ba don gadar ba, Kogin bai qetaruwa cikin sauqi. Tun tun tuni wani Bature mai hankali ma'aikacin Gwamnati, ya ba da shawara, manyansa kuma masu hankali suka yarda da shawarar tasa cewa wata rana duk yadda aka yi sai an yi hanyar jirgi daga bakin teku ta wajen fuskar Jihar Gabas zuwa Jihar Arewa, don a sami kaiwa ga burin da ke akwai na sa hanyar jirgin qasa ta rarratsa qasar nan.

"Aka kuma daidaita shawarar cewa inda hanyoyin jirgin za su haxu, sai su haxu dab da Kogin Kaduna a sashen Kudunsa, don kuwa a lokacin babu wanda zai iya dagewa ya ce sai ya ga an gina gada ta uku a kan kogin nan. Xaya gadar da yake ta zama tilas a yi ta, tun daga lokacin da aka daidaita shawarar haxa hanyar jirgin Gwamnati, kamar yadda a ke kiran hanyar jirgin Ikko zuwa da hanyar Nijeriya ta Arewa. Ita kuma ta Arewa ana kiranta Hanyar jirgin Baro zuwa Kano, wadda a kanta ne aka yi wa Kogin Kaduna gada a Kaduna.

"Sojan Nijeriya ta Arewa duk a lokacin a Kakuri suke (wato kusa da tashar da aka gina gadar). Ba a daxe ba sai aka mayar da wurin ya zama hedkwatar soja, da farko

don sojan Nijeriya ta Arewa, daga baya kuma don sojan duk Nijeriya baki xaya. Irin wannan shiri ya nuna yadda Turawan Ingilishi ba su cika dogara ga soja ba wajen tsaron zaman lafiyar qasar nan. Sai a lokacin yaqin da ya wuce ne kaxai shugaban soja, wanda a lokacin Manjo-Janar ne, ya tafi inda hedkwatar Gwamna take ya zauna, ba a Kaduna ba, inda waxanda ya gada, waxanda dukkansu Kanar Kanar ne suka zauna. Nan ne fa cibiyar qasar nan da ta fi dacewa da soja. In har za a kwashi soja zuwa wani wuri, nan da nan za a iya yin hakan nan, sai kurum a sa su cikin xaya daga cikin jiragen nan masu bin hanyoyin nan uku da ke tashi daga Kaduna, fiye da kowane wuri.

"Lugga, an koya masa aikin soja, kuma goguwa ta yau da kullum ta sa ya zama qwararren soja, don haka koda yaushe tunanin abubuwa irin waxannan suna cikin zuciya tasa. Kuma shi gwanin iya mulki ne, don haka ya san muhimmancin samun hedkwata wadda ta dace don a ji daxin tafiyar da mulkin. Ko da yake ita ce ya fi so da can da farko, amma daga baya sai ya ga ba ta dace da abubuwan da aka zave ta dominsu ba. Zariya ko Kano su ne kuma ya kyautu a duba a gani ko za su da ce. Dukkansu dai hanyoyi sun wadace su, suna kuma da yanayin qasa mai kyau, wato a bisa ganin Bature, Zariya ita ce ta fi dacewa. Amma Lugga sai ya ga ai kuskure ne a kafa hedkwatar Gwamnati a garin da wani Sarkin Yanka yake. Irin duk yadda Gwamnati ta kai ga ba da bayani, wannan ba zai hana Sarkin jin cewa ya fi sauran Sarakuna daraja ba, wato ya kauce wa tsarin darajar Sarakuna ta da, don saboda damar da ya samu don zuwan baqi da suka zo da nasu sabon mulkin. Kuma bisa gaskiya shi ma Sarkin ba zai so a kafa masa hedkwatar Gwamnati ba a garinsa, domin sai ya rasa sukuni, tun ba ma idan ya ga Gidan Gwamnati ya fi nasa kwarjini ba. Da Jos ya kamata kuma a tuna da ita, amma a lokacin nan hankali bai kwanta ba, don haka ba a cika ambatonta ba.

"Abin da na faxa game da wannan cikin Majalisa, shi ne: ..".Mu dai in don mu, ni da abokan aikinsa, da yake ba mu goge qwarai ba da xaukar irin nauyin nan na aikin Ministoci, muna matuqar farin ciki da ya zamana a nan Kaduna ne za mu yi aiki, ba a wurin da waxansu al'amura da su ke namu ne irin na da za su yi ta kutso mana kai ba. Hasali ma dai an ajiye mu a wuri wanda za mu sami babbar dama ta yin tunani, da yin aiki, don amfanin jama'ar Jihar nan baki xaya..."

"Lugga dai ya daidaita shawara zai yi gine-gine a karkara, wurin da za a yi gine-ginen kuwa shi ne, a kusa da gadar Kogin Kaduna, inda soja suka riga suka kafa ofisoshinsu. Aka yi ta gardandami a kan wajen da ya kamata a yi gine-ginen, har a qarshe dai aka yarda a yi su a sashen arewacin kogin, wato inda muke nan yanzu.

"Wajen yawan mutane kuma, kullum Kaduna qaruwa take yi. Cikin 1939 akwai mutane 4,336 a Kaduna, cikin 1960 kuwa yawansu ya kai 73,346. Tsawon Kaduna kamar mil goma sha xaya ne daga arewa zuwa kudu, kamar mil biyar daga gabas zuwa yamma. Wurin har yanzu qaruwa yake ta yi, ga alama kuwa zai ci gaba da qaruwar ne. Wurin da aka keve a can sashen kudu don yin masana'antu yana nan yana ta samun sana'o'i suna ta kafawa. Irin waxannan wuraren yin sana'o'i suna sama wa mutane ayyukan da za su yi, haka kuma irin na Gwamnati, da na Gwamnatin Jiha, da na Tarayya, dukansu kuwa kowa ya kan zo tare da iyalansa. Duk kuwa wajibi ne su sami abincin da za su ci, don haka garin kullum qaruwa yake yi.

"Har zuwa 1956 harabar Kaduna duk a qarqashin lardin Zazzau take, En'e ta Zariya har tana ma da xan ofis a wurin, ma'aikatan Sarki, a qarqashin shugabansu guda, su ne su ke tafiyar da komai da komai. Wannan a qarqashin ikon *Razdan* na Zariya ne, wanda ya kan ma zo rangadi ya xan shaqata a nan. Ko ta yaya kuma Laftanan-Gwamna ba zai rasa sa bakinsa cikin harkokin garin nan da ke dab da shi ba, musamman game da tsara garin, da gine-gine na garin. Musamman kuma game da tabbatar da zaman lafiya, abu ne kuwa wanda yake mai rikitarwa wani lokaci, kuma abu ne wanda ya shafi Sakataren Mulki da Ofishinsa. Waxanda ba su cewa uffan sai Ministoci, waxanda yake hedkwatarsu ce kuwa.

"Gari fa ya waye, lokaci ya yi da za a fayyace komai filla-filla game da al'amarin nan, wanda wajen aikatar da shi ya ma fi yadda na bayyana rikitarwa. Sai muka daidaita shawarar mu kafa Yankin Qasar Hedkwata, wanda zai haxa da duk wuraren da aka riga ya aka yi gine-gine da kuma muhimmin filin jirgin saman nan. Wato za a vulguce wannan ne daga lardin Zazzau, a sanya shi qarqashin ikon wani Minista (ni ne kuwa ba wani ba). Mai tafiyar da mulkin wannan Yankin Qasar Hedkwata zai kasance wani Babban Ma'aikacin Gwamnati ko En'e-En'e. Wurin da ma dai can 'yan Sanda ke duba shi, musamman wajen da gine-ginen Gwamnati su ke, cikin gari kuma 'yan Doka. Tun da babu 'yan Doka sai 'yan Sanda a yanzu, waxanda kasancewa tasu qarqashin Gwamnatin Tarayya zai jawo wata wahalar zuwa gaba.

"Zai sami wata hukuma mai ba shi shawara – ba kuwa hukuma xaya ba, amma hukumomin ba su da ikon zartar da komai, sai dai su ba da shawara kurum. A nan mun yi koyi ne da yadda a ke yi a waxansu alqaryu, kamar su *Canberra* da *Washington*, amma mu ba mu zurfafa al'amarin yadda su suka zurfafa ba, domin kuwa a can mazaunan wurin ba su da 'yancin yin komai, a matse suke.

"Shirin Dokar kafa Yankin Qasar Hedkwatan nan a gaba ne aka zartar da shi. An yi 'yar mahawara, amma sai abokan hamayya suka tsaya da maganganunsu kan yawan 'yan Majalisa da irin ikon da suke da shi, waxannan kuwa abubuwa ne masu

sauqi da za a iya maganinsu nan da nan. Ba su soki muhimman abubuwan da suka kamata su soka ba, misali kamar maganar kiyaye dokoki da odoji a ga ana bin su sosai, ko kuma maganar kuxi. Da masu abin da suka saba yi ke nan, idan an yi gabas, su su yi yamma.

"Don a qara xan hanzari kaxan, wajibi ne in ce shekara biyar da aka yi ana ta aiki tuquru sun nuna mana cewa sake tsari ya wajaba, kuma a lokacin da nake rubutun nan, ana nan ana ta tanadin sababbin shirye-shirye waxanda za su xora ta kan hanyoyi amintattu saboda nan gaba. Ni da abokan aikina mun mai da sha'anin nan na Kaduna muhimmi qwarai. Ba fa hedkwatarmu ce kaxai ba, inda gidajemmu da ofisoshimmu suke, a'a har ma da ganin cewa zuwa gaba ita ce za ta zama hedkwatar ciniki ta qasan nan Nijeriya ta Arewa. Tamkar dai yadda na faxa wajen bikin buxe wani garejin mota a nan. Ga abin da na ce:

"Na tabbata cewa Kaduna ita ce farfajiyar wurin ciniki a duk Nijeriya ta Arewa. A nan ne lokaci-lokaci Wakilan Jama'a su kan zo don su yi shawara a Majalisa. A nan ne kuma Sarakuna, waxanda ke yi wa Majalisunsu na En'e jagora, su kan kuma zo su yi shawarwari a tasu Majalisar da sauran taro iri-iri. A nan ne kuma shugabannin ma'aikatun Gwamnati suke da zama. Kuma a nan ne Gwamnati ke daidaita shawarar irin kayan aikin da za ta saya don kyautata ci gaban Jihar nan. Mu, Gwamnatin dake zaman kanta, mun qawata garin da kyawawan gine-gine, muna kuma tunanin qara waxansu nan gaba. Muna kuma sa rai mu ga manyan Kamfanonin ciniki su masun yi haka nan. Amman don gine-gine su kaxai ai ba su isa ba. Wajibi ne a tafiyar da al'amuran hedkwatar nan yadda ya kamata, jama'ar da ke cikinta su kasance suna masu farin ciki da wadatar zuci."[1]

Sir Ahmadu Bello

[1] Ahmadu Bello, RAYUWATA, shafi na 209 zuwa 213

QADDAMARWA

A 'yan shekarun baya, mahaifiyata Hajiya Amina Isa ta sha fama da ni don in je wajen wasu Dattawa waxanda suke buqatar saduwa da ni. Amma a duk lokacin da ta buqace ni da zuwa na kan kawo mata dalilan cewa aikace-aikace irin namu na masu xalibtar koyon aikin likita sun yi mani yawa, don haka sai in roqe ta da ta ba ni 'yar dama ko lokaci da zan samu lokacin zuwa. Dalilin kuwa da take son zuwa na wurin waxannan Dattawa, shi ne domin qara danqon zumunci a tsa kanin mu. Su dai waxannan Dattawa sun yi zamani da mahaifinta Sarkin Alaro Malam Isa, don haka su na son ganin zuriyarsa.

A wannan lokaci ina xalibta Koyon Aikin Likita a Jami'ar Ahmadu Bello amma na kan zo gida Kaduna kusan kowane qarshen mako. Wata rana sai mahaifiyata ta ce lallai sai in tafi wajen wani Dattijo mai suna Malam Tanimu Zariya don in gaishe shi. Malam Tanimu Zariya ya yi murna da zuwa na, nan da nan sai na shaqu da shi, domin na kan je wajensa yana ba ni labarin kakana malam Isa Sarkin Alaro da sauran manyan mutanen da suka yi zamani da shi tun a garin. Dungurun (tsohuwar Hedkwatar Arewa). ni kuma na kan bai wa mahaifiyata irin waxannan labaru da nake samowa, sai na fahimci ina faranta mata rai da su, don haka sai na duqufa wajen yin binciken labarun mutanen da, wato na wancan zamanin Turawa. Ita ma mahaifiyar tawa sai ta riqa tura ni wajen Dattawa daban-daban don nemo tarihi. Abu dai kamar wasa, sai ga shi cikin xan qanqanin lokaci na yi bincike mai zurfi game da yadda aka taso daga Dungurun aka kuma kafa garin Kaduna.

Bayan da na gamsar da mahaifiyata da ire-iren waxannan labarun da na binciko, sai na shiga bai wa abokaina kanun waxannan labarai, su kuma sai suka ce ai babu abin da ya fi kyau kawai sai in rubuta wannan labari a littafi domin na baya su qaru, abin da ban tava tunanin yi ba! Su waxannan abokai nawa sai suka qara mani qwarin gwiwa wajen yin wannan namijin aiki, inda a cikin su, Abdulhamidu Aliyu ya bani shawara da qara qarfin gwiwa, ganin na kama aiki na wallafa wannan littafi. Sai kwatsam Allah da ikonSa ga ni na shiga tsundum ina binciken tarihin garin Kaduna!

Amma shiga wannan aiki da na yi ba shiri, sai naga ashe kitse na yi wa ganin rogo! Na farko dai rubuta tarihin gari kamar Kaduna abu ne mawuyacin gaske, saboda an yi shekara da shekaru ana cusa wa mutane ra'ayoyi iri-iri, kowa sai

faxar abin da ya so yake yi game da Kaduna ba tare da wani qwaqqwaran bincike ba. Domin haka ne garin ya taso ba shi da wani muhimmin tarihi.

Na biyu kuma, bunqasar da garin ya yi cikin hanzari wanda ya bai wa kowa mamaki, domin haka abu ne mawuyacin gaske a ce an yi littafi a yanzu wanda zai kawo komai da komai game da garin, wato kammalallen tarihi. Na ukunsu kuma, ni kaina ba ni da lokaci da kuxin da zan xauki xawainiyar wannan aiki saboda matsayina na xalibin, Koyon Aikin Likita wato *Medical Student*. A cikin wannan hali ne Malam Tanimu Zariya ya qarfafa min gwiwa wajen yin yin aiki, wanda ya ce zai taimaki jama'a. Saboda haka, a cikin wannan matsayi lokaci na shiga bincike da rubuta tarihin wannan gari. Na yi amfani da hutun qarshen mako daga ranakun Juma'a zuwa Lahadi, na kuma yi amfani da kuxin abincin da nake samu wajen mahaifina wajen yin wannan littafi.

Dalili mafi qarfi, shi ne la'akari da zamani, saboda a wannan qarni na ashirin, abubuwan da ake samu a bakin tsofaffi, wato *Oral source of history* ba su isa madogara kawai wajen rubuta tarihi ba, dole ne sai an yi amfani da abubuwan da suke a rubuce wato *Written source of history*. Ka ga dole ne a yi bincike mai zurfin gaske. Na yi amfani da waxannan hanyoyi, inda na samu ikon yin tone-tonen abubuwan da suka shafi mutum da kuma nazari a kan su wato *archaeology* da na yi a garin Afaka.

Domin in tabbatar da gaskiyar abin da na samu daga tsofaffi, na bi qwaqqwafin abubuwan daidai gwargwado. Na tattauna da tsofaffi masu ximbin yawa, na kuma yi tafiye-tafiye don tabbatar da gaskiyar abubuwan da na samo. Na tafi Birnin Kano da Katsina da Borno da Jos da Minna. A lokacin wannan bincike, na saurari hirar da aka yi da tsofaffi daban-daban a gidajen rediyo, don haka kusan duk abubuwan da na rubuta suna da hujjoji qwarara.

Bugu da qari na karanta Jaridu da Mujallu masu ximbin yawa game da Kaduna ko Arewacin Nijeriya. A xakin bincike da ke Kaduna, wato *National Archives* na yi amfani da fayiloli masu yawa da suka shafi wannan gari. Haka kuma na yi amfani da littafan Tarihi masu yawa a *Arewa House* da *National Library* da suke Kaduna. Ban sami sukunin zuwa xakin ajiye kayayyakin Tarihi na Sojoji ba. Koda yake na ji akwai wasu kayayyakin da Dakarun Arewa suka yi amfani da su a yaqin Duniya na farko!

Kamar yadda na faxa a baya bincike ya xauke ni zuwa wuraren da ban tava zaton zan je ba, haka kuma na sadu da mutane masu yawa da ban tava mafarkin saduwa da su ba. Na kawo abubuwa masu dama da suka shafi Arewa domin

amfanin matasa masu zuwa nan gaba, saboda Ilimi yana daxa qaruwa, kuma masu qwazo na qara zurfafa bincikensu a kan waxansu al'amura na tarihi. Ba ina nufin cewa wannan shi ne kammalallen tarihin Kaduna kamar yadda za a zata ba, akwai wurare da yawa da ba a zurfafa bayani a kansu ba, wasu kuma da yawa ba a kawo su ba, abin nufi dai a nan, shi ne wurin da littafin ya gaza, to, ina fatan ya zama matashiyar wani binciken nan gaba.

Wannan littafi zai bayar da labarin mazauna wannan wuri wato Kaduna tun daga wajejen shekaru dubu kafin vullowar Nasara (Turawa) har ya zuwa zamaninsu. Amma saboda tarihi yauqi ne da shi, na tavo kaxan daga cikin abubuwan da suka faru bayan mulkin Turawa har ya zuwa wannan lokaci da muke ciki a yanzu. Wannan tsarin zai nuna yadda Hausawa da Fulani da Gbagyi (Gwari) da Barebari suka taho a lokaci daban-daban zuwa wannan wuri. Saboda haka tun kafin zuwan Turawa, waxannan qabilu ke zaman tare, zaman ka zo - na zo. Ka ga bai kamata a jingina garin Kaduna ga wata qabila ita kaxai ba, kamar yadda ake yi a halin yanzu.

Ina fata wannan littafi zai wayar wa da jama'a kai sosai game da garin Kaduna da mutanen da ke cikinta. Na wallafi wannan littafi a lokacin ina xalibi (Medical Student), a Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariya domin bayar da tawa gudunmawar wajen duk ayyukan da za su kawo wa qasarmu ci gaba.

Bayan shekaru ashirin da fitowar wannan littafi, sai jama'a suka nemi a qara buga shi saboda ya yi qaranci sosai har ma ba a samunsa a xakunan karatu da shagunan littafai. A dalilin haka, sai ya zama wajibi a qara buga wannan littafi, a kuma faxaxa shi daidai gwargwado; musamnan a wannan zamani da na qarni na ashirin da xaya da jama'a suka fahimci amfanin tarihi sosai.

Alqur'ani Mai Tsarki, kuma Littafi Mabuwayi wanda ya yi bayani a kan komai, shi ya bai wa tarihi muhimmanci sosai. Masana sun ce kashi xaya cikin biyar na wannan Littafi Mai girma tarihi ne domin mutane su sami abubuwan koyon darussa daga cikin tarihin xaixaikun mutane da kuma na alqaryoyin da suka shuxe. Ka ga ke nan tarihi abu ne mai muhimmanci sosai. Kada fa mu ce abubuwan da suke faruwa a yanzu ba tarihi ba ne, don kuwa duk abin da ya yi farko, zai yi qarshe wato zai zama tarihi. Don haka ne ma ake rubuta tarihin mashahuran mutane da na garuruwa daban-daban domim jama'a su sami abin koyi. Tarihin gari kuwa yana bayani ne a kan jama'ar da suka kafa garin da wahalolin da suka sha da kuma yadda suka yi mu'amula da juna har garin ya bunqasa.

Bunqasar gari da buwayarsa, tasirin jama'ar da suka kafa garin ne tun fil-azal waxanda suka shimfixa kyakkyawan harsashin ci gaban garin da jama'arsa. Su waxannan jama'a sun samu shugabanni waxanda suke masu gaskiya da tsoron Allah tare da karsashi. Don haka ne suka haxe kan jama'arsu suka kuma ba su jagorancin da ya kawo masu ci gaba. An kuma dace jama'ar ba su yi wa juna kitififi da makida ba, waxansu daga cikin muggan halayen jama'a da ka iya zama kutungwilar hana ci gaba. Ha kan na iya faruwa in an sami bambance-bambancen al'adu da na addini. Amma ba bambance-bambancen qabilu da al'adu ne abin gudu ba, a'a, qin amfani da fahimtarsu shi ne, domin bambance-bambance na da amfani ne wajen samun sauqaqe wa da juna, wanda shi ne matakin farko wajen ci gaban jama'a.

Tasowa da bunqasar garin Kaduna cikin hanzari, wani nuni ne da cewa ba kafuwa ce marar asali ba, don kuwa garin da mazauna cikinsa sun yi qarfi da suna wajen mulki da tattalin arziqi da sha'anin addini, ba a Nijeriya kaxai ba, a duniya baki xaya. Bambanci tsa kanin xan Arewa da xan Kudu ko kuma tsa kanin Musulmi da Kirista mazauna wannan gari, bai hana su ci gaba ba. Har an kai ana cewa idan Kaduna ta kwana da mura, to, Nijeriya za ta tashi da zazzavi. Tun fil-azal Kaduna gari ne inda qabilu suka tarkatu, yana kuma fama da qaruwar jama'a a kullum inda albarkatocin qabilu iri-iri daga ko'ina suka haxu suna mu'amala da juna don samun ci gaba.

Amma duk da haka a kan sami varkewar rikice-rikice a tsa kaninsu waxanda ke haddasa asarar rayuka da varnar dukiya, musamman a lokacin tavarvarewar arziqin qasa da ta shugabanci. A zaman tare, harshe da haqori kan samu savawa amma duk da haka suna nan tare. Haka ma mazauna garin Kaduna rikice-rikice na siyasa da addini da makamantansu ba su kawo cikas ba, ko kuma mummunar barazana ga zamantakewar juna ba.

Tasirantuwar garin Kaduna a Nijeriya na da nasaba da bunqasar wannan yanki tun kafin zuwan Turawa. Qabilu daban-daban sun taso a lokuta daban-daban, sun zauna a gavar dajin Doka inda aka kafa garin Kaduna da kuma gavovin kogin Kadduna inda garin ya samo sunansa.

A ranar 8 ga watan Oktoba na shekarar 1988 a xakin taro na Gidan Shawara wato (Lugard Hall) da ke Kaduna ya cika maqil da jama'a. A wannan rana ce a ka yi bikin qaddamar da littafin da kake karantawa. Uban taro shi ne mai Martaba Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris CFR, bai samu harlarta ba, amma ya turo wakilinsa, da Babban baqo na musamman shi ne mai girma Gwamnan Mulkin

Soja na Kaduna Kanar Abdullahi Sarki Mukhtar, bai samu halarta ba amma ya turo wakilinsa, Kwamishinan Ilimi, Alhaji Shehu Ladan. Babban baqo mai jawabi shi ne Alhaji Yusuf Maitama Sule, Xan Masanin Kano. Babban baqo mai qaddamarwa shi ne Alhaji Ahmadu Aruwa bai sami halarta ba, amma ya turo wakilinsa, Alhaji Abubakar Siniya. Alhaji Waziri Gula xaya daga cikin dattawan Kaduna shi ya zama Uban biki.

Taro ya yi armashi sosai, an kuma tattauna matsalolin zamantakewar jama'a a wannan gari. Alhaji Balarabe Musa, tsohon Gwamnan Jihar Kaduna yana xaya daga cikin manyan baqi da suka tofa albarkacin bakinsu. Tsohon Gwamnan Kaduna ya yi bayani ne a kan darajar muqamin Sarkin Alaro wato (Labour Leader), a zamanin Turawa. Inda ya ce muqami ne babba a idon Turawan Mulki, saboda suna bai wa ma'aikata da shugabanninsu girma qwarai da gaske. Alalmisali, shimfixa hanyar jirgin qasa da leburori suka yi daga garin Baro zuwa birnin Kano aiki ne na ci gaban qasa. In ba ma'aikata babu ci gaban qasa. A wancan zamani leburori su ne ma'aikatan farko da suka ba da gudunmawa gaya wajen kawo ci gaban Arewa, saboda haka sarautar Alaro muhimmiya ce.

Shi kuwa Alhaji Yusuf Maitama Sule, Xan Masanin Kano bayan ya qayatar da taro da kalamai masu kyau, sai ya gabatar da wani qaulinsa na asalin Hausa inda ya ce Hausawa asalinsu daga Habasha da ke *Ethiopia* suka fito, daga wannan kalma ce ma 'Habasha' aka samo 'Hausa'. An kuma tava siyasar Arewa inda Alhaji Sabo Bakin Zuwo, Tsohon Gwamnan Jihar Kano ya yi jawabi mai ma'ana sosai a kan shugabancin 'yan Siyasar Farko da ta lokacinsu a zamanin shugabancin Alhaji Shehu Shagari.

Shi kuwa Alhaji Shehu Ladan, Kwamishinan Ilimi na jihar Kaduna kuma wakilin Gwamna, bayani ya yi a kan zamantakewar musulmi da kirista a lokacin su Sardaunan Sakkwato. Ya ce irin wannan zaman lafiya da lumana da suka yi dole ya zama abin koyi da misali ga mazauna garin Kaduna da Nijeriya baki xaya. Shi kuwa Furofesa Bashir Ikara, Daraktan Cibiyar Binciken Tarihi na gidan Sardauna wato *Arewa House*, bayani ya yi a kan amfanin bincike da rubuce-rubuce. Amma shi Alhaji Hassan Sani Kwantagora mai Mujallar *Hotline* bayani ya yi a kan kyawawan halayen Sardauna Gamji xan qwarai a zamaninsa. Ta kowane fanni taron bikin qaddamar da littafin Tarihin Garin Kaduna ya yi tasiri sosai.

Ana cikin jawabai da kalamai masu ma'ana da farantawa sai Alhaji Yusuf Maitama Sule, wato babban bako mai jawabi ya laqaba mani suna mai farantawa.

Ya sa mun suna "Yusuf Nadabo Xa Mai Albarka." Babu shakka wannan laqabi ya share mani hawaye har ma baqin cikin da suka addabe ni daga wahalhalun bincike da buga littafin har ya zuwa wannan rana ta bikin qaddamar da shi, sai suka kau daga gareni. Ina mai roqon Allah Ya taimake ni in amsa wannan suna mai farantawa mai sa himmatuwa ta hali da aiki. Wannan biki sai ya zama tambari a garin Kaduna har ma da sauran qasashe da yawa. Saboda 'yan jarida da sauran kafafen yaxa labarai sun yaxa shi sosai.

Ana cikin wannan hali sai na kai ziyara ga mai Martaba Sarkin Zazzau domin in yi godiya saboda amsa gayyata ta da yayi. Ina gurfane a gabansa sai Sarkin Fadan Zazzau, Alhaji Ahmadu Fatika ya gabatar da ni gaban Sarki da kalami kamar haka:

"Mai Martaba, Yusuf Nadabo ya yi qoqari wajen wallafa wannan littafi, Tarihin Garin Kaduna. Ya yi bincike mai zurfi ya kuma kafa hujjoji masu qarfi. Wani abu kuma, shi ne ya yi wannan aiki ne a lokacin yana xalibin koyon aikin likita. Wannan ba qaramin aiki ba ne kuma Zazzau ta amince da wannan littafi na sa."

Da Sarkin Fadan Zazzau ya gama jawabinsa, sai Mai Martaba Sarkin Zazzau, ya sanya mani albarka. Ya kuma umarceni da in ci gaba da rubuce-rubucen da za su kawo wa jama'a ci gaba.

Bayan an kwana biyu da yin wannan ziyara, sai na kai wa Alhaji Nuhu Bamalli, Magajin Garin Zazzau ziyarar ban girma. Na tafi da abokina Hamidu Aliyu, inda na same shi a ofishinsa da ke Maxaba ar Bugun Littafai da ke Zariya wato (Gaskiya Corporation Zaria). Magajin Gari ya na cike da murmushi sai ya ce, "Yusuf Nadabo kai ba likitan lafiya ba ne, likitan tarihi ne." Ni kuma sai na amsa da cewa "Ranka ya daxe, ni likitan lafiya ne kuma mai sha'awar tarihi!"

Shi ma Magajin Gari marubuci ne, ya wallafa littafai ya kuma fassara wasu littafai don bunqasa Ilimi a Arewa. Samunsa da muka yi, a wannan mashahuriyar maxaba a ya nuna cewa yana nan a kan harkar havaka Ilimi duk da girman shekarunsa. Ya ba da babbar gudunmawa wajen Talifi a wannan maxaba a, wadda ta wallafa da fassara littafai masu yawa a Arewa. Babu shakka ya yi maraba da ziyarar mu har ma ya ce: "Allah Ya yi ma albarka, Zazzau ta amince da littafinka."

Wata rana bayan 'yan shekaru da bikin qaddamar da littafin, na je gidan Alhaji Adamu Yusuf ma'aikacin Rediyon *BBC* dake Kaduna sai na tarar da Alhaji Garba

Xanshagamu, shugaban qungiyar Mutanen Kaduna *Kaduna Peoples Association* (KAPA) a wancan lokaci. Sai na gaishe shi amma bai gane ni ba. Ganin haka ne sai qanena Sarkin Dutse, Alhaji Shu'aibu Balarabe Abdullahi, ya ce da shi, "Dr. Yusuf Nadabo ne ke gaishe ka." Nan da nan sai ya kama hannuna cikin farin ciki ya kuma ce da ni: "Littafinka ya taimaki 'yan Kaduna. Mun samu muqamin 'yan asalin jiha wato *Indigeneship* mun kuma sami Qaramar Hukuma (Local Government) 'ya'yanmu kuma na samun tallafin karatu *Scholarship*, Allah Ya yi ma albarka." Wato Kaduna ta amince da littafina.

Na ji daxi da waxannan kalamai, sun kuma share mani hawaye. Na kuma tuna a shekarun baya a lokacin ina xalibin koyon aikin likita, na zo ganawa da 'yan kwamitin ba da tallafin jiha wato 'Interview' wajen neman *Scholarship* sai 'yan kwamiti suka tambaye ni, kai Nadabon Katsina ne ko Nadabon Funtuwa? Na ce, "Ni Nadabon Kaduna ne." Sai suka ce "ai babu Nadabo a Kaduna!"A wannan lokaci ba a raba lardin Katsina da lardin Zazzau ba wato ba a qirqiro jihar Katsina daga Kaduna ba, 'yan Kaduna kuma na shan wuya wajen samun tallafin tallafin karatu. A wannan lokacin tantacewar ne a shekarar 1979 sai aka dakatar da ba ni tallafin jiha tun da iyaye na daga Kano suka fito.

Qwamfa! Sai ga shi Allah Ya huwace min na zama likita har na rubuta littafin da ya taimaka wa 'yan Kaduna har ma suna samun *Scholarship* don tallafar xalibi lokacin xalibtarsa ba tare da wahala ko tsangwama ba. Sadoda littafin ya taimaka wajen fahimtar mutanen Kaduna da yadda suka zo wannan gari. Na kuma gode Allah da Yasa na ga amfanin littafin ga Zazzau da jama'arta, don kuwa littafin ya taimaka wajen ba mai haqqi haqqinsa, saboda fahimtar juna abin da babu shakka ya kawo sauqaqewar fahimtar juna.

Ko da Zazzau ta amince da littafin, amma ko kaxan qabilar Gbagyi ba ta yarda da shi ba. Saboda na ce "Kaduna ba garin Gbagyi ba ne." Sun ce wannan kalami ya vata masu rai sosai saboda an yi shekaru aru-aru ana cewa, "Kaduna Garin Gbagyi," sai gashi na qaryata wannan batu a rana tsaka. Saboda haka sai suka zarge ni da na qwace "garin Gbagyi na ba Fulani." Ko da yake wannan zargi maras tushe ne, amma duk da haka ya so ya haddasa tarzoma a wannan lokaci. Saboda har bore a kan littafin suka so su yi abin da da ya ta da hankalin jami'an tsaro sosai. Dalilin haka ya sa Daraktan 'yan Sandan ciki wato (State Security) Alhaji Ahmad Suka da kwamishinan 'Yan sanda na jihar Kaduna Alhaji Bappa Jama'are suka gana da ni a kan zargin na rubuta littafin da zai kawo tashin hankali a Kaduna.

Na kare kaina daga duk zargin da ake mani da hujjoji masu qarfi da gamsarwa. Na kuma shaida ma shugabannin jami'an tsaro da cewa littafina zai kawo zaman lafiya da fahimtar juna, ban kuma rubuta shi domin in zalunci wata qabila ko mabiya wani addini ba. Saboda na rubuta tarihi ne abisa abubuwan da bincike ya nuna, ba bisa son rai ba. Don kuwa cewa "Kaduna Garin Gbagyi," ne ai ra'ayi ne ba tarihi ba. Duk wanda zai binciki tarihin Kaduna zai ga garin ba shi da nasaba da wata qabila ta qut-da-qut. Domin kuwa ba a tashi garin Gbagyi, ko Fulani ko Hausawa ba wajen kafa wannan gari. Kamar yadda Miss Miller ta bada shaidar cewa babu gari a wannan daji sai zakoki a shekarar 1907. Saboda haka, yin tunziri a kan littafi ba shi ne abin yi ba. Abin da ya kamata a yi shi ne a qaryata littafin da hujjoji masu qarfi da za su nuna yadda garin Kaduna ya zama garin Gbagyi muxlaqan. Mai girma, Alhaji Bappa Jama'are ya gamsu da wannan bayani nawa har ma ya ce, "in na sami sukuni zan halarci bikin qaddamar da wannan littafi naka." Shi ma Daraktan *State Security Service* ya gamsu da bayanai na sosai ya kuma buqaci in ba shi kwafin littafan don ya kai ma mai girma Gwamna Kanar Sarki Mukhtar.

Rashin tarihi illa ce babba ga al'umma sosai idan aka dubi Hausa-Fulani mazauna Zangon Kataf da Mazauna garin Jos da babu wanda zai nemi ya kore su da sunan baqi 'yan sami wuri zauna. Saboda gudun barin baya da qura ya sa na qara zurfafa bincike da qara qarfafa hujjoji da ke nuna Kaduna ba ta da alaqa da wata qabila amma tana da alaqa da qabilun da suka kafa garuruwa da ke kusa da dajin doka, wanda shi ne dajin da aka kafa Kaduna. Domin qabilu su fahimci juna sosai su kuma qara danqon zumunci a tsakanin su.

Tunda aka yi bugun farko na littafin a shekarar 1988, ba a sake buga shi ba, wannan ya sa littafin ya yi qaranci sosai, har ma ba a samunsa a xakunan karatu da shagunan sayar da littafai. Jama'a kuma na buqatarsa sosai, ganin haka na ga ya dace da a sake buga shi a wannan karo. An qara faxaxashi da wasu labarai da bayanai da ba su sami shiga a bugun farko ba. An kuma qara bada wasu labarai muhimmai da suka shafi Arewa domin marubuta su sami abubuwa masu yawo a kan tarihin jihar Arewa.

Tarihin garin Kaduna, tarihin Turawan Mulki ne da Sarakuna, da Sojoji da 'yan Siyasa da Ma'aikata, a lokuta daban-daban, waxanda suka yi wa Arewa ayyukan ci gaba. Kaduna, Arewa ce a dunqule don haka tarihin garin ya zama tarihin Arewa ne a taqaice. Saboda haka, sai aka faxaxa shi da labarai da jawaban wasu shugabannin Arewa da kuma gudummawar da suka bayar wajen ciyar da

Arewa gaba. A Kaduna aka aiwatar da ayyukan da suka havaka Jihar Arewa da Hedkwatarta.

A garin Kaduna ne aka tafiyar da Mulkin Mallaka (Colonial Rule) da mulki ta kan Sarakuna wato (Indirect Rule), saboda haka aka kawo taqaitaccen tarihin Mulkin Mallaka da illolin da suka haifar wa Arewa, musamman illolin mulki Ta kan Sarakuna wato (Indirect Rule). Waxannan illoli ne suka ragargaza Arewa suka rarrabata sashi-sashi kowane sashe yana gaba da hamayya da wani sashe, ta yadda Arewa ta kasance a yanzu Taron Tsintsiya shirim ba shara, ta yadda jihohin Gabas da Yamma suka sami galabar mallake ta. A taqaice Mallakar 'yan Kudu ta maye gurbin mallakar Turawa daga shekarar 1966 har ya zuwa yanzu. Na fahimci yadda Mulkin Mallaka ya rarraba kan jama'ar wannan jiha da sauran jihohi bisa tsarin nan na farraqa kan jama'a don a ji sauqin mallakarsu. Har ila yau a qarqashin wannan mulki, an yiwa Arewa juyin-waina na sama ya koma qasa.

A wannan shiri ne Sarakuna da Alarammomi aka maida su qasa. Haka kuma shirin Turawa na "Na gaba ya koma baya" ne ya xora qananan qabilu bisa manya a wannan shiri na kyaun Rawa Na gaba ya koma. A dalilin haka ne na zurfafa na kuma yawaita bada bayani a kan Illolin Mulkin Mallaka da na Mulki ta kan Sarakuna waxannan illoli ne ke wa Arewa cin-gara har yanzu. Saboda haka ya zama tilas a sake sabon fasalin mulkin Arewa ba a riqa bin tsarin Mulkin Mallaka sau da qafa da sunan ci gaba ba.

Shirin 'na gaba ya koma baya' da na 'Juyin Waina' sun birkita Arewa ta fannonin mulki, da addini da Ilimi da siyasa da kasuwanci. Sarakuna a zamanin (Indirect Rule) sun sami kansu a mawuyacin hali. A qarshen wannan mulki wanda illolinsa har yanzu ke ragargazar Arewa, Sarakuna da Makarantun Allo sun tavarvare matuqar gaske saboda Sarakuna sun rasa ikonsu, makarantun Allo kuma sun rasa muhimmancinsu. Qarfi da yaji aka murqushe dukkan al'adun kawo ci gaban jama'a, musamman ta fuskar sana'o'i da kuma raunana kyawawan xabi'u da al'adun Arewa.

A fannin siyasa kuma firimiyan Arewa Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato, ya fahimci munin Mulkin Mallaka ya kuma hangi qarshen al'amura a Arewa. Saboda haka ne ya shimfixa manyan ayyuka a Kaduna da Arewa baki xaya duk da cewar tsarin Mulkin Mallaka yana hana ruwa gudu a wancan zamani. A dalilin haka ne ya qarfafa Majalisar Sarakuna ya kuma tafi da ita kafaxa da kafaxa da Majalisar Wakilai, a kyakkyawan shirinsa na Sarakuna a siyasa. A wannan shiri, Sarakuna sun taka rawar gani wajen yin ayyukan raya qasa da jin

daxin jama'a. Da fika fikan waxannan majalisu ne Sardauna ya yi wa Arewa ayyuka muhimmai ya kuma dunquleta ta zama Haxaxxiyar Arewa wadda ake kira da Turanci *Monolithic North*. Sarakuna sinadarai ne kuma danqon haxa kan Arewa.

Na yi kambun-baka da cewa Arewa ba za ta samu haxin kai da ci gaba ba sai Sarakuna sun shiga siyasa ka'in da na'in. Kowace qasa na yi wa tsarin Dimukuraxiyya gyarar fuska domin aiwatar da shugabancin da ya dace da addini, xabi'u da al'adun jama'a. Firimiyan Arewa ya nuna misali abin koyi domin ya jajirce wajen tafiyar da siyasa ba tare da ya yi watsi da kyawawan al'adu da xabi'un jama'ar sa ba. Domin kuwa mulkin dimukuraxiyya bai wajibta tarayya a al'adu da xabi'un jama'a ba, musamman a qasa mai qabilu da al'adu iri-iri. Ai kyaun Dimukuraxiyya kowane tsuntsu ya yi kukan gidansu ba a tursasa shi ya yi kukan gidan wasu ba da sunan ci gaba. Saboda haka, bin tsarin Siyasa Samfurin Ingila ko na Amurka ba tare da yin la'akari da bambance-bambancen halaye da zamantakewar jama'a ba halaka ne!

An qayatar da littafin da hotuna na tarihi da na shugabanni. Saboda su zama tarihi a hotuna. Haka kuma an tsakuro kaxan daga cikin gudunmawar da 'yan Siyasar farko suka ba da don ci gaban Arewa tare da gudunmawar da Sarakuna suka bayar a lokuta daban-daban, tun daga zamanin Shehu Mujaddadi har ya zuwa zamanin mulkin Turawa da na Siyasar farko. Ya kamata ne a yi masa qwarya-qwaryar faxaxawa wacce za ta qunshi tarihin "Kaduna Sabuwa" amma hakan ba zai yiwu ba saboda wasu dalilai. Tarihin Kaduna sabuwa wato (Modern Kaduna Town) zai samu a nan gaba, in Allah Ya yarda. Har ila yau ya kamata a juya wannan littafi zuwa harshen Turanci. Saboda yin haka ya zama wajibi.

A qoqarin qara faxaxa wannan aiki na ziyarci wurare da dama na kuma yi nazari gwargwado game da Ilimin boko da tasirinsa a kan jama'ar Arewa. Na kuma yi nazari game da halin jama'ar wannan jiha da yadda matsayin Sarakuna da Makarantun Allo suka kasance a wannan zamani domin na bi salsalar tushen gaba da su. A binciken da na gudanar na karanta littafai na tarihohin mulki da na zamantakewar xan-Adam. Na kuma karanta qasidu da jaridu masu yawan gaske musamman na shekarun baya daga shekarar 1939 zuwa ta 1966, haxi da fayilolin mulki a Gidan Sardauna (Arewa House) da Gidan Tara Kayan Tarihi na Kaduna (National Archives Kaduna).

Waxannan karance-karance sun daxa gasgata wasu abubuwan da na gani ko na samu a wajen hira da tsofaffi dattawa da tsofaffin ma'aikata. Zurfafa binciken

da na yi ya qara wa wannan littafi qarfin hujjoji da saitin alqibla. Saboda wannan littafi a tsaye ya ke daram wajen bayyana yadda aka kafa garin Kaduna ba tare da an tashi wata qabila ba, saboda haka ne garin ba shi da nasaba ta qut-da-qut da wata qabila. Haka kuma wannan littafi yana nuni *bil-haqqi* da gaskiya a gina sabuwar Arewa an ci amanar Sarakuna da makarantun Allo!

Lokacin abu ayi shi. Littafin ya qunshi abubuwan tarihi masu yawa waxanda aka kawo su domin su zama matashiyar bincike a kan su ko kuma su zama dalilin zaburar da masanan tarihi wajen yin katafaren aiki a kan su. Amma duk da haka littafin bai kammala ba, akwai abubuwa da dama da ba a samu kawosu ba ko kuma zurfin bincike bai kai garesu ba. An kawo abubuwan tarihi ne domin kada a yi asararsu a cikin tarihi wanda sauye-sauyen zamani ke haifarwa. Komai Ilimin mutum da wanda ya fi shi. Saboda haka duk kurakuran dake wannan littafi, gazawata ce saboda haka nake roqon duk wanda ya ga wani kuskure, to, ya taimaka a gyara shi domin samar da tabbataccen tarihi. Yanzu ya kamata mu qara sanin tarihin gudunmawar da shugabannin baya suka bayar wajen ci gaban jama'a. Mu daina wasa da tarihi don kuwa ana iya amfani da shi a yaqe mu. Masu hikima kuma sun ce: "Wanda bai kiyaye tarihi a qirjinsa ba, ba zai iya rabe zaqin rayuwa daga xacinta ba, kuma wanda ya kiyaye labarun waxanda suka shuxe ya tara shekaru a kan shekarunsa."

Alhamdu Lillahi

Dr. Yusuf Nadabo Abdullahi

Ramadan 1430 A.H

Agusta/Saumba, 2009

GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangiji Maxaukakin Sarki wanda Ya ba ni ikon wallafa wannan littafi, Ya kuma azurta ni da mutanen da suka ba ni kyakkyawan taimako wajen yin wannan muhimmin aiki.

Yana da wuya a rubuta littafi irin wannan don bayyanan tarihin gari kamar Kaduna ba tare da an sami taimako daga waxanda suka bayar da tasu gudunmarwa ba, a lokuta daban-daban. Saboda haka ya zamo dole in miqa godiya ta ga waxanda suka taimaka wajen yin wannan aiki. Da wuya a ambaci kowa da kowa, amma akwai wasu fitattu waxanda ya kamata a tuna da gudunmawar da suka bayar.

Ina miqa godiyata ga Malam Tanimu Zariya wanda ya kwaxaitar da ni da yin wannan aiki, ya kuma ba ni kyakkyawan goyon baya. Ina godiya ga Malam Mamman Maidala'ilu Kano saboda shawarwarin da ya ba ni. Haka kuma ina godiya ga waxannan abokai nawa saboda qara mani qwarin gwiwa da suka yi a lokacin wallafa wannan littafi: Abdulhamid Aliyu da Adamu Muhammad da Alhaji Xanjuma Muhammadu Baqi da Malam Idris Umar, da kuma Malam Aliyu Abubakar.

Ba zan manta da waxannan mutane ba saboda nuna goyon baya da suka ba ni a lokacin wannan aiki: Dr. Tukur Abdullahi da Wazirin Dikwa Alhaji Abba Habib, da Alhaji Mahmud Aminu Sakataren Sarkin Kano, Alhaji Ado Bayero da Alhaji Shu'aibu Maqarfi da Alhaji Ibrahim Hamisu. Haka kuma ina godiya ga Sarkin Maqera, Alhaji Xalhatu da Limamin Maqera, Alhaji Yusuf da Alhaji Muhammadu Tanko Maqera da Madaki Daru Kakuri-Kurmin Gwari da Alhaji Usman Baba Gwanki.

Ina miqa godiyata ta musamman ga dukkan ma'aikatan Jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo saboda sha'awa da suka nuna wajen wannan aiki tare da taimakon da suka bayar, malam Sani Saleh wanda ya xauki xawainiyar nazari da gyaran baqaqen wannan littafi, da kuma Habu Musa da Benjamin Abu waxanda suka buga da keken rubutu. Haka kuma ina godiya ga Alhaji Adamu A. Yusuf da Alhaji Tanko Aliyu. Ahmed Abdulmalik Mani shi ne wanda ya taimake ni da xaukar wasu hotuna.

A wajen faxaxa wannan aiki na samu qarfafa gwiwa daga Farfesa Abdullahi Mahdi, Darektan *Arewa House* wanda ya karve ni da hannu biyu ya kuma ba ni taimakon da nake buqata a Arewa *House*, ya kan qarfafa mini gwiwa da cewa:

"Likita, in ka gaji da *Medicine* ka zo *Humanities* ka huta." Na samu shawarwari masu amfani daga Farfesa A.M. Yakubu da qarin karsashi daga Barista Ibrahim B. Ahmed, da Yusuf Abdullahi Qofar-Sauri. Alhaji Mamoon Baba Ahmed, Xan Hausa, shi ne wanda ya taimaka matuqar gaske wajen fassara wasu qasidu masu yawa daga Turanci zuwa Hausa. Ina kuma godiya ga ma'aikatan Gidan Sardauna wato *Arewa House* saboda sun ba da gudunmawa gaya wajen faxaxa wannan aiki. Godiya ta musamman ga Malam Abdullahi A. Maradun, Malam Musa Muhammad Salisu da Malam Usman Sulaiman da sauran ma'aikatan wannan Gida. Ina godiya ga Hon. Justice Umar Abdullahi (Rtd), CON., Walin Hausa, saboda sha'awar da ya nuna ga wannan aiki. Ina kuma godiya ga Alhaji Abdulqadir Balarabe Musa, Tsohon Gwamnan Jihar Kaduna saboda shawarwarin da ya bayar wajen wannan aiki.

Haka kuma ya zama wajibi har ila yau in miqa godiya ta musamman ga dukkan mutanen da nayi hira da su da waxanda suka aiko mani da rubuttatun bayanai ko hotuna. Ina godiya ga qanina alhaji Shu'aibu Balarabe Abdullahi, Sarkin Dutse, saboda taimakawa da suka yi wajen nemo hotuna. Mista Emmanuel Oloye, da Abduljalal Yusuf Nadabo, da Malam Hashim Mohammed Saleh ne suka yi gyara da buga littafin a *computer* a lokuta daban-daban.

Daga qarshe ina miqa godiya ta musamman ga matata Hajiya Badiya da 'ya'yana – Amina (Nasara), da Abduljalal da Fatima (Golden Girl), da Zulqarnaini, da Maryam da A'isha saboda haquri, da taimako, da goyon bayan da suka bani a lokacin da na riqa kaxaice masu alokutan jigilar tattara bayanai da rubuta wannan littafi. Allah Ya saka wa dukkan waxanda suka taimaka wajen wallafa wannan littafi da alheri, amin.

Na gode wa Allah Ubangijin talikai. Allah Ya qara wa Annabi Muhammadu (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) daraja da wasilah, amin summa amin.

QUMSHIYA

SHAFI

Gabatarwa	iv
Sanya Albarka	vi
Matashiya	ix
Qaddamarwa	xiii
Godiya	xxv
Qumshiya	xxvii

KASHI NA XAYA

Jihar Arewa	1
Lardin Zazzau	6
Kogin Kaduna	10
Garin Afaka	11
Vullowar Qabilar Gbagyi	14
Vullowar Fulani	19
Garin Kinkinau	22
Garin Kawo	25
Vullowar Barebari	27
Garin Barnawa	28
Barnawa Cibiyar Sarakunan Zazzau	31
Garin – Maqera	38
Kurmin Mashi	40
Rigacikun	42

KASHI NA BIYU

Me Ya Kawo Turawa Arewa?	44
Mulkin Kama-Karya	44
Turawa 'Yan Yawo	47
Cinikin Bayi	49
Turawan Kamfani	50
Yarjejeniya Da Sakkwato	51

Wasoson Kama Wurare 53
Turawan Mishan 54
Takun Saqa 61
Reverend Bargery 63
Maraba da Baqi 65
Kasuwar Auduga 69
Mulkin Mallaka a Arewa 72

KASHI NA UKU
Hedkwatocin Arewa 80
Garin Lakwaja 80
Garin Jebba 81
Garin Dungurun 83
Mulki ta Kan Sarakuna 85
Bunqasar Dungurun 90
Naxin Sarkin Alaro 92
Bikin Daba A Dungurun 101
Aikin Diga 104
Gina Gadar Jirgi 106
Neman Sabuwar Hedkwata 117
Gaskiya Sunanta Gaskiya 121
Budurwar Qasa 123

KASHI NA HUXU
Kafa Garin Kaduna 136
Aikin Gina Kaduna 138
Tasowa Daga Dungurun 157
Kafa Sabon Gari 164
Gini Da Tsarin Layi 175
Shugabannin Farko 183

KASHI NA BIYAR
Shari'a Da Dokokin Gari 193
Tsabtar Gari Da Muhalli 205
Samar da Ruwan Sha 210

Samar da Wutar Lantarki 214
Nazariyya a Kan Zamantakewa a Arewa 229
Allo Xaukakar Arewa 233

KASHI NA SHIDA
Arewa A Yaqin Duniya 242
Sojojin Afirka Ta Yamma 242
Yaqin Kamaru Da Is'afrika 244
Yaqin Duniya Na Biyu 250

KASHI NA BAKWAI
Sarautar Sabon Garin Doka 315
Kafa Kaduna Yankin Hedkwata 320
Magajin Gari Muhammadu Sambo 331
Sarkin Sabon Gari Malam Baqo 332
Sarkin Zazzau Muhammadu Aminu 334
Sarkin Zazzau Shehu Idris 338
Havakar Sabon Gari 343

KASHI NA TAKWAS
Kafuwar Unguwanni 349
Dalilin Kafa Unguwanni 349
Kafa Tudun-Wada 359
Hanyar Mota Da Maqabarta 364

KASHI NA TARA
Kaduna Hedkwatar Arewa 380
Gwamnonin Kaduna 384

KASHI NA GOMA
A Zamanin Sardauna 405
Sir Ahmadu Bello 407
Ayyukan Ahmadu Bello 429
Kwaleji Ta Ahmadu Bello 437
Masaqar Kaduna 452

Jaridar New *Nigerian* 463
Babban Asibitin Kaduna 464

KASHI NA GOMA SHA-XAYA
Aiki Da IBada 476
Sardauna ya yi Kira Ga Samari 481

KASHI NA GOMA SHA-BIYU
Ba 'Yan Arewa Jan Arewa 508
Sukurkucewar Al'amari 508
Arewa ta Zama Balbela 521
Ba 'Yan Nijeriya Ian Ragamar Nijeriya 526

KASHI NA GOMA SHA-UKU
Sarakuna A Siyasa 572
Qa'dojin Siyasa 575
Majalisar Sarakuna 588
Dabar Sir Macpherson 590
Matsalolin Majalisar Siyasa 603
Matsalolin Majalisar Sarakuna 613
Tarukan London 625

KASHI NA GOMA SHA-HUXU
A Zamanin Turawa 667
Rasuwar Sarkin Katsina Dikko 669
Jawabin Sabon Sarki 677
Maraba da Eric Thomastone 679
Bankwana da Sir Eric 693
Maraba da Sir Sharwood Smith 696
Rasuwar Sarkin Kano Abdullahi Bayero 703
Maraba da Sarkin Kano Sunusi 709
Jawabin Razdan Na Sakkwato 717
Maraba da Sir Gawain Bell 725
Gwamnatin Sir Gawain Bell 727

KASHI NA GOMA SHA-BIYAR

Ziyarar Sarauniyar Ingila	757
Jawabin Firimiya	775
Jawabin Sarauniya	777
Liyafa a Gidan Gwamna	779
Liyafa a Gidan Shawara	783
Jawabin Gwamna	791
Qasar Nan ta Samu Xaukaka	794

KASHI NA GOMA SHA-SHIDA

Kaduna A Siyasar Farko	797
Tsohuwar Guguwar Siyasa	797
Dalilin Kafa NPC	802
Alqawuran NPC	805
Sardauna ya yi Kira ga 'Yan Arewa	806
Dalilan Kafa NEPU	807
Rikirkitaccen Zamani	820
Daula Xaya Iko Uku	826
Siyasar Qiyayya da Tsageranci	832

KASHI NA GOMA SHA-BAKWAI

Mulkin Kan Jihar Arewa	838
Farkon Sabon Yanayi	838
Shagulgulan Samun Mulkin Kai	846
Qasaitacciyar Daba	847
Alamar Arewa	848
Kare Lafiyar Jama'a	851
Ziyarar Duke da Duchess	854
Bukin Mulkin Kai a Sakkwato	857
Qasaitacciyar Liyafa	866

KASHI NA GOMA SHA-TAKWAS

'Yancin Nijeriya	868
Ziyarar Wazirin Ingila	868
Gari ya Waye Safiya ta yi	877

Gimbiya ta Gode wa 'Yan Arewa 890
Fushin Abubakar Imam 891

KASHI NA GOMA SHA-TARA

Cibiyar Yaxa Addini 899
Kaduna Bariki 899
Makarantar Islamiyyar Farko A Arewa 902
Makarantar Islamiyyar Farko a Kaduna 907
Qungiyoyin Addinai 914

KASHI NA DAYA

Jihar Arewa

Jihar Arewa ta fi kowace jiha girma a Nijeriya. Qasa ce mai yawan mutane; kuma ita ce qasar da ta fi kowace girma a Afirka. Tarihinta daxaxxe ne, wanda larduna masu yawa suka yi dauloli a lokuta daban-daban; shekaru aru-aru kafin rahoton Leo Africanus na tafiye-tafiye a cikin Yammacin Sudan kusan farkon qarni na goma sha-shida, wato qarni na 16 bayan Annabi Isa (amincin Allah Ya tabbata a gare shi).[1]

Jiha ce mai bambanci mai ban mamaki. Lardunan da suka fi zama Arewa sosai suna da daxaxxen tarihi. Kusan tarihinsu ya kai shekaru dubu, ko fiye da haka. Lardunan da suka fi zama Arewa, su ne Sakkwato, da Katsina, da Kano da Barno, kusan suna busasshiyar qasa ce a kusa da hamada suna shiga cikin yashin sahara a hankali. Amma duk da haka, lokacin ruwan sama, hanyar ruwa suna cikowa a wurare da yawa, ya mayar da wurin ya zama qasa mai albarkar noma da kiwo, manomi ya yi shuka a dausayi. Kuma a nan ana kiwon garken shanu, da tumaki, da awaki, waxanda aka qiyasta sun kai fiye da miliyan biyar. Fata da qiraji suna cikin abubuwa masu amfani da ake fita da su daga Jihar Arewa kuma jar fatar awaki ta Sakkwato (wadda ake yin fatar Morocco) shahararriya ce a duniya.

Wannan qasa na da faxi sosai; tun daga mil xari biyar (500 miles) daga kan iyakar Kudu da Arewa da kuma mil xari bakwai (700 miles) daga Gabas zuwa Yamma, Jihar ta rufe murabba'in mil dubu xari biyu da tamanin da xaya da xari takwas da saba'in da biyu (281,872 miles); har da qasar Amana ta Kamaru ta Arewa kan iyaka ta Arewa ta yi iyaka da qasar Faransa ta Nijar, Yamma kuma da *Dahomey*, Gabas kuma da Jamhuriyar qasar Kamaru. A Kudu, xan yankin qasa wanda zurfinsa mil xari da ashirin (120) zuwa mil xari da tamanin ne (wanda ya haxa Jihar Gabas, da Jihar Yamma ta Nijeriya) sun tsare Jihar Arewa daga Teku Kudancin yankin Jihar Arewa, waxanda suka haxa da lardunan Ilori da Kabba da Neja da Binuwai suna da daji sosai. Waxannan larduna su ne qasar wurare da Fulani suka yaqa a Kudu a farkon qarni na goma sha-takwas.

Ko da yake Arewacin Jihar Arewa busasshen wuri ne, duk da haka suna da kogunan da ke da amfani. Kogin Kwara wanda jirgin ruwa na iya zuwa har Lakwaja ya ratso daga Kudu zuwa Gabas fiye da mil xari biyar (500 miles) a cikin Jihar a kan hanyarsa ta zuwa teku. Kogin Binuwai, wanda jirgin ruwa na iya

[1] Kai Da 'Yancin Nijeriya, shafi na 9

zuwa har Garwa a cikin Jumhuriyar Kamaru a lokacin damina ya ratso daga Gabas dai-dai irin wancan tsawo. Duka waxannan koguna suna da hannuwa; manya a ciki su ne; kogin Sakkwato (tsawonsa mil xari uku da tamanin (380 miles) suna shiga cikin kogin Kwara; da kuma kogin Gongola tsawonsa kusan mil xari uku da tamanin (380 miles) wanda ya shiga cikin kogin Binuwai. Akwai kuma qanana da yawa masu ban sha'awa. A hannuwan kogin Binuwai, akwai kuma koguna da yawa masu yin Arewa ta Gabas, waxanda suka faxa a cikin Tafkin Chadi.[1]

Mil hamsin daga Arewacin kogin Binuwai tsawon qasa ya kai qafa dubu biyu daga ruwan teku, wurin da ya fi kowane, tsawo a qasar kuza tsawonsa qafa dubu shida ne. Qasar kuza nan a ke samun kuza wadda tana kashi xaya daga cikin kashi biyar na kuzar da a ke samu a duniya baki xaya; kuma kusan duk kuzan nan da ake kira *Columbite* ta duniya duka a nan a ke samunta.[2] Arewa qasa ce mai ximbin arziqi.

Sahara ita ta raba Jihar Arewa da sauran duniyar da kai ya waye da Arewa. A Kudu kuma wanxanda ya tsare ta, su ne manya-manyan kogunan nan biyu inda qudan tsando ya hana kiwon dawaki da shanu, wannan ya sa Arewa ta zauna a voye a cikin qarni da yawa. Jihar Arewa, qasa ce mai bambanci, mai ban mamaki. Allah Ya azurta ta da yawan jama'a da qasa mai albarka cike da ma'adinai iri-iri. A lokacin damina, wurare da yawa na cikowa; ruwan sama ya mayar da wuraren wajen noma da shuke-shuke a bisa dausayi mai albarka, ana shuka auduga da gyaxa da sauran kayan gona masu amfani.[3]

Tun fil azal an san Jihar Arewa da qasaita wajen sana'a; an san ta da bunqasa wajen ciniki; an san ta wajen iya tafiyar da mulkinta. Duk da bambance-bambancenta yawan mutanenta suna qaruwa har isarwa kansu, sun kuma sami ci gaba a fannoni masu yawa. Tun a zamani mai tsawo, Jihar Arewa matattarar malamai ce kuma cibiyar 'yan kasuwa daga kowane gari ko qasashe. Ita qasa ce mai ya kana.

Mutanenta suna da hali, jama'arta su masun san ya kamata. Haka kuma mazaunanta jarumai ne, kuma muzakkarai. Sarakunanta qasaitattu, malamanta mashahurai. Tana da 'yan kasuwa maxaukaka masu sufuri da shige da fice shekaru masu yawa kafin zuwan Nasara; kai tun kafin Turai ta fito daga qangin talauci da jihilci, Arewa ta yi suna a duniya. Larabawa 'yan kasuwa da Turawa 'yan yawo; sun ratsa hamadarta a kan raquma don su zo wannan qasa mai albarka. Sun kuma rubuta abubuwan mamaki da suka gani da abubuwan ci gaban xan-

---

1 *Kai Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na 9

2 *Ibid*. shafi na 9-10

3 *Ibid*

Adam da suka qaru da su. Babu shakka mutanen Jihar Arewa, lallai su yi alfahari da addininsu da al'adunsu; su kuma zama masu kishi da Jiharsu; inda komai ya ji ban da tsiya.

Saboda su na da abubuwan da za su nuna wa duniya na tarihi wanda kowa zai iya alfahari da shi. Akwai abubuwa da suka fito fili sosai su ne, Hausawa masu gaskiya ne kuma jarumai ne. Da Turawan Mulki da Turawan Kamfani, wato Turawan (Royal Niger Company) da suka zo qasar nan duk sun fi yarda da Bahaushe, game da yin al'amura na riqe amana. Misali duk Turawan Kamfani na farko da suka fara zuwa qasar nan, sai suka shiga duba irin qabilar da za ta fi dacewa da muhimman ayyukan nan biyu, aikin soja da xan sanda. Suka duba, suka duba, amma sai suka ga Bahaushe ya fi riqe amana. Qarfin zuciyar Bahaushe game da riqon amana, shi ne ya sa ya fi kowace irin qabila dacewa.

"Kuma abin mamaki, ashe ba tun yanzu aka soma xibar waxansu daga cikin sojojinmu, ana kai su Ingila wajen shagalin biki idan za a yi ba. Ko cikin shekarar1887 an kwashi waxansu sojoji Hausawa, su 42, aka kai su Ingila, a wajen bikin taya Sarauniya Victoria murnar cikarta shekaru sittin a gadon Sarauta. Wannan ma abin alfarma ne ga Bahaushe. "[1]

Cikin kusan miliyan goma sha-tara (19 millions) na mutanen da ke zaune a Jihar Arewa, an qiyasta cewa fiye da kashi uku a cikin kashi biyar Musulmi ne. Kusan kashi biyu daga cikin kashi uku na Musulmin sun haxa da Hausawa, da Barebari, da Fulani. Mafi yawan waxannan qabilu uku suna zaune a Lardunan Kano, da Sakkwato, Katsina, da Barno, da Zariya da Adamawa – Ko da yake za a iya ganin waxannan qabilu a ko'ina a cikin Jihar. Farkon Fulani ba sananne ba ne. Abin da aka sani kawai shi ne sun fito daga qasar Masar qarnoni da yawa da suka gabata, waxansu suka yiwo Yamma zuwa Duwatsun Futa-Jalo kusa da Senegal, waxansu kuma suka nufi Kudu, har sun tava isa qasar Hausa, suka dangana a kan irin zamansu, can ba a rasa ba, su kan auri matan wurin ko su aurar da 'ya'yansu ga mutanen wurin, waxansu har yanzu suna riqe da launin jikinsu. Bararo, kamar yadda a ke kiransu, sun qi haxuwa da mutanen da kansu ya waye.

Barebari, waxanda su ne qabilu na uku wajen yawa, kusan suna zaune a cikin lardin Barno. Su haxe-haxen qabilar Larabawa da na Hamitic, da Baqin Mutum ne, kuma can wani lokaci da ya wuce su ne suka kafa daular Kanem. Barebari sun ce tun shekaru 700 da suka wuce suke aikawa da xalibai zuwa Masar, an kuwa gan shi a cikin wani littafi da a ke kira *Memories Sur I'Egypte* wanda ya tabbatar da haka: A cikin shekara ta 640 A.H (1242 A.D.) su (wato mutanen Kanem) suka

---

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa* " Na Abdulmaliki Mani wanda Madab'ar Gaskiya Zariya ta buga a shekarar 2007, shafi na 27.

gina a cikin garin *Fustat* (Masar) kwaleji, wadda a ke kira *College Ibn Rashis*. Wannan kuwa sananniyar Jami'a ce ta *Al-Azhar*.[1]

Barebari sun tsare hare-haren mayaqan Fulani shiga cikin qasarsu a farkon qarni na goma sha-takwas, amma kuma kusan qarshen wannan qarni, an faxa wa Barno da yaqi, a wannan lokacin suka vata qasar. Wanda ya aikata haka kuwa wani bawa ne da a ke kira Rabe wanda ya gudo daga Sudan, tare da mabiyansa, yaci Barno, ya fitar da Sarki, kuma ya kashe Shehu, shi kuma kansa aka kashe shi a wajen yaqi da Turawan Faranshi kusa da Tafkin Chadi a cikin 1900.

> *A bisa xaukaka da daraja a duniya, Allah Ya azurta 'yan Arewa da baiwa iri daban-daban. Ana iya cewa da Allah Ya halicci duniya, Ya fi son qasar Makka wato Saudi Arabiya inda a nan ne aka haifi Annabi Muhammadu (S.A.W) mafificin halitta baki xaya, wanda aka aiko da Addinin qarshe wato Addinin musulunci. Daga wannan yanki mai Tsarki da Albarka, sai qasar Falasxinu da ke Gabas Ta Tsakiya. Wannan yanki ya zama na biyu wajen daraja a Fadar Allah, saboda a nan ne Allah Ya aiko da dubban Annabawa Yahudawa. Don haka wannan yanki ne mai Albarka.*
>
> *Nijeriya ta Arewa, ita ce ta zo ta uku a daraja a Fadar Allah saboda wannan yanki shi ne Lambun Alqur'ani a duniya. Allah Ya azurta Arewa da miliyoyin Mahaddatan Alqur'ani wanda babu kamarsa a duniya baki xaya. Alal misali, bincike ya nuna lardin qasar Barno kawai na da mahaddatan Alqur'ani da yawansu ya ninka yawan da ake da su a Gabas Ta Tsakiya baki xaya. Saboda haka Arewa lambun Alqur'ani cewadda Allah Ya azurta da mashahuran malamai waxanda suka yi fice a fannoni daban-daban a duniya. Manzo Allah (S.A.W) Ya ce, "Malaman qarshen zamaninsa dai-dai suke da Annabawa Yahudawa na wancan zamani. " Saboda haka ana iya cewa Arewa ce ta biyu a maxaukakiyar daraja. Shahararrun maluman Arewa sun taimaka gaya wajen havaka ilimin Addinin musulunci a duniya. A wannan yanki ne Shehu Usman Mujaddadi ya bayyana a qarni na goma sha-takwas, ya kafa Daular Usumaniyya wadda ta taimaka gaya wajen havaka Addinin musulunci da ci gaban xan-Adam. Don haka ya kamata mu san kanmu domin mu yi ayyukan da suka dace da mu.*
>
> *A cikin tsakiyar qarni na goma sha-takwas, sai Addinin musulunci ya yi sanyi, sai da baki kawai a ke faxarsa, ba a aiki da*

[1] *Kai Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na p10 & 12

shi, to, don haka sai Shehu Usmanu xan Fodiyo ya fara jihadi wanda shi ne dalilin kafa daular Fulani.

Waxansu sauran muhimman qabilu a Arewa, su ne Tivs da Idoma na cikin Lardin Binuwai. Mafi yawansu ba Musulmi ba ne, da Nufawa da Gbagyi waxanda duk yawancinsu suna cikin Lardin Neja, waxanda Fulani suka yaqa, waxanda duk yawancinsu Musulmi ne; Igala, da Igbirra da kuma Yarbawan Arewa qabilu biyu na farko suna cikin lardin Kabba a Yarbawan Arewa kuwa suna cikin lardin Ilorin da Kabba. Su waxannan qabilu suna addini iri daban-daban–waxansu sun fi son musulunci, waxansu daga Arnanci aka juyar da su zuwa Mishan.[1]

Sauran mutanen da ke cikin Jihar sun haxa da qabilun Arna, waxansu ma yawansu bai wuce 50,000, ba kuma babu waxanda yawansu ya kai 60,000. Su waxannan Arna suna zaune a wurare mafi duwatsu a Arewa, kamar a Qasar Kuza, ko kuma a kan duwatsun da suka yi iyaka da Kamaru, suna zaman qauyanci. Farkonsu ba sananne ba ne, amma wataqila suna daga cikin qabilun da suka gudo daga hare-haren mayaqa daga Arewa da Yamma don su sami wurin vuya a cikin duwatsu, inda suke zaune tun lokacin. Mazaje ne, masu qoqarin aiki waxanda a hankali aka juyar da su zuwa ga addini, da kuma hanyar zaman Turawa, kuma, a nan gaba, ba shakka za su xauki matsayinsu a Majalisar Arewa.[2]

Akwai lokatai biyu a Jihar Arewa, lokacin rani, da lokacin damina. Su waxannan da muka faxa duka, an qididdige su a cikin 'yan makwanni. Lokacin rani, a can Arewacin Arewa, akwai zafi qwarai da gaske, ma'aunin sanyi ya kan faxo har xigo 12 daga cikin xari. A 'yan makwanni kaxan a cikin watan Disamba da Janairu ma'aunin zafi da sanyi ya kan nuna sanyi kaxan da rana, amma da dare ya kan nuna har ya kai dai-dai da na qasar Turai. Abin da ke rubuce qarancin sanyi shi ne ma'aunin ya nuna xigo 40 zuwa 45 na Faranhayit, kuma ba safai ba ya kan dawo xigo 37. Tun farkon wannan qarni, an sha samun lokacin ma'aunin sanyi, ya nuna sanyin ya kai lokacin da ruwa zai daskare a Katsina.Tun daga watan Fabrairu har lokacin da aka fara ruwan sama (wanda ya bambanta ga yin Arewa) da rana ma'aunin zafi kan qaru da yawa har a wurare da yawa, ya kan kai

---

1 *Kai da 'Yancin Nijeriya*, shafi na 10 & 12

2 *Ibid*. shafi na 12

xigo 100. Amma saboda raguwar zafin lokacin da rana ta faxi, dare yana da sanyi sosai.[1]

Lardin Zazzau

A cikin tsofaffin lardunan Arewa, akwai lardin Zazzau; wanda shi ma ya yi ficewajen albarkar qasa mai qabilu iri-iri da shugabanni mashahurai. Wanda ya kafa masarautar Zazzau kuma Sarki na farko a daular mulkin Have shi ne Gunguma. Have sun fara zama ne a wani gari da ke qasar Zazzau a yanzu da ake kira Turunku. Waxannan Have su ne ake kira asalin Hausa kuma suna da al'adu daban-daban. Sannan sun karkasu a wurare daban-daban. Ana jin kuma tun kafin zuwan Gunguma akwai mazaunin jama'a a wurare masu yawa da ke kusa da juna. A xaya daga cikin waxannan tsofaffin wurare suka kafa Birnin Zariya, sauran wuraren sun haxa da Madarkaci, da Kufena, da Tukur-Tukur. Haka kuma tun a wancan zamanin za munna a kwai ma'adinai na qarfe, ana kuma sarrafa su wajen yin makamai.[2] Saboda arziqin wannan sana'a ne ma ya sanya qabilu kamar Gbagyi, da Kurama da Kadara da Kaje suka taho zuwa wajen dutsen Kufena suka zauna.[2] Wannan gari na da ganuwa mai tsohon tarihi.

Tarihi ya nuna cewa Sarakunan Have sittin ne suka yi zamani kafin yaqin Jihadin Fulani ya vullo a shekarar 1804. Ga sunan waxanan Sarakuna: Gunguma, Matazu, Tumsa, Tamrasu, Suleiman, Nasau, 'Dan Zaki, Nayuga, Kauci, Nunaki, Mushalkwui, Kayau, Najida, BushaiKuri, Kirari, Jajunuku, Kana, Muhammadu Abu, Gudumasu Kana, Tukira, Kunasu, Baka Turunku (Bakwa), Amina, Ibrahim, Karma, Kafau, Bako, Aliyu, Ismaila, Musa, Gabi, Hamza, Abduka, Buraima, Aliyu, Muhammadu Rabbu, Ibrahim Busuku, Su kana, Aliyu, Ibrahimu, Muhammadu Rabbu, Alu, Bako Dan Mowa, I'shaku, Buraimu Asha Kuka, Bako Dankana, Muhammadu Uban Bawa, Muhammadu Dangabi, Muhammadu Gabi, Muhammadu Abu, Bawawa, Yunusa, Baku ba Mutum Shehu, Aliyu, Muhammadu Maigamo, I'shaku Jatau da Maku (Makau).[3]

Waxannan su ne jerin sunayen Sarakunan Have sittin da suka yi zamani kafin vullowar Yakin Shehu Mujuddadi. A cikin su akwai Musulmi waxanda suke, bin Addinin musulunci kafin varkewar yaqin jihadi a shekjarar 1804.

Have sun fara zama ne a Turunku, daga baya suka kafa garin Zariya. Gunguma shi ne ya fara sarauta, a mulkin Have, ya kuma fara zama a Turunku, garin da ke Kudu maso Yammacin Zariya. Wannan tsohon gari ne mai ganuwa.

---

1 *Kai Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na p 12

2 Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isiyaku*. *The Great Emir of Zazzau*, shafi na shafi na 4-5.

3 *For the Zazzau Emirate Bicentenary Anniversary of the Sokoto Caliphate* (1804-2004) programme, shafi na . 16-17.

Amma tun kafin jihadin Shehu Usmanu, Sarkin Zazzau Jatau ke musulunci.[1] A dalilin kasancewarsa Musulmi ba ya yin al'adun maguzanci irin na jama'arsa Maguzawa. Ya kuma taimaka wa Fulani masu bin Addinin musulunci a lokacinsa. Bayan rasuwarsa, sai aka naxa Makau sarautar Zazzau, shi Bamaguje ne, domin haka sai ya dawo da al'adun Have. Da wannan Sarki ne 'yan Jihadi suka gwabza yaqi wajen kafa mulkin Daular Usumaniyya a lardin Zazzau.

Lardin Zazzau, shi ne mafi girma a duk lardunan qasashen Hausa, yana kuma xaya daga cikin larduna masu tsohon tarihi. Zazzau ta samu girman lardi ne saboda yaqe-yaqen da Amina Sarauniyar Zazzau ta yi. Wannan ya sa Muhammadu Bello ya ce a cikin littafin nan '*ImFaqul Maisuri*: "Abubuwan mamaki sun faru a cikin tarihin qasashen Hausa bakwai, amma mafi al'ajabi shi ne mallakar qasa Mai girma da Allah Ya baiwa Amina Sarauniyar Zazzau. Ta ci duk qasashen Hausa da yaqi, saboda haka Katsinawa da Kanawa na kai mata haraji. Ta yaqi Bauci da sauran qasashen da suke Kudu da Yamma, sai da mulkinta ya dangane da bakin teku. "

Idan aka dawo kan faxin qasa kuwa, sai a ga Amina sarauniyyar Zazzau; 'yar Bakwa Turunku ce ta faxaxa wannan lardi. Ta yi wannan gawurtaccen aiki ba da lalama ba amma ta tsinin mashi. Marubuci C.R Niven cewa ya yi: "Bakwa yana da wata 'ya da ake kira Amina, wadda lallai ta isa a ambace ta. Babu inda ba ta tafi ba a qasashen Hausa, don haka har yanzu akwai tsofaffin garuruwa masu sunanta. Ko da yake sunanta ba ya cikin lissafin Sarakunan Zazzau amma lallai ta sarauce ta har shekaru talatin da huxu, kuma mulkinta ya kai har bakin Kwara da Binuwai. Da Kwararrafa da Nufe duk sun ba ta gandu. "[2]

Don haka ne a zuwan Turawa, lardin Zazzau yana da faxin gaske, ga shi kuma maqil da qabilu iri-iri. Amina Sarauniyar Zazzau, ita ce babbar 'yar Sarkin Zazzau Bakwa-Turunku. Yaqe-yaqen da ta yi ta ciwo wa Zazzau manya-manyan qasashe. Ta mallaki mutanen Kwararrafa (Jukunawa) da qasar Nufawa. Sarakunan Nufawa na kawo mata goro qwarya xari (100) da fixiyayyun bayi arba'in kowace shekara. A lokacinta ne aka fara cinikayya a tsakanin mutanen kudancin wannan qasa. Amina ta yi shekaru wajen talatin da huxu tana mulki. Ta rasu a garin Idah a bakin kogin Neja. Amma da shigowar Turawa Arewa, saboda wasu dalilai, sai suka rage faxin wannan makeken lardi.

A watan Fabrairu na shekarar 1900, rundunonin sojoji guda biyu suka dunfari birnin Zazzau; xaya daga garin Wushishi qarqashin *Manjo Morland*, xaya kuma daga Binuwa a qarqashin Kanar *Lowry Cole*. Waxannan rundunonin sun haxu a

---

[1] Abbas M. Fagachi, *Mai martaba Sarkin Zazzau, Alhaji Shehu Idris CFR*, shafi na XIII

[2] Duba littafi, *Labaran Nijeriya*, Na C.R Niven, Norla Zariya ta buga, a shekarar 1955, shafi na 15

Girku, daga nan sai suka runtuma zuwa birnin Zazzau, inda suka yi dafifi a wajen ganuwa, a lokacin mulkin Sarkin Zazzau Kwasau.

A shekarar 1901, ana cikin zullumin yaqi da Turawa sai ga mummunan labari tafe, Sarkin Kwantagora Ibrahim na Nagwamatse zai farma Zariya da yaqi. Da jin haka fa, sai Sarkin Zazzau Kwasau ya nemi taimako wajen Gwamna Lugga da ya taimake shi da sojoji; nan da nan sai aka aika masa da wani kamfani daga sojojin *West African Frontier Force* (WAFF). Tunda aka girke waxannan sojoji ba su bar Zariya ba, sai a shekarar 1913 inda suka tashi zuwa garin Barnawa.[1]

Ko da guguwar yaqi ta kwaranye, sai a watan Maris na shekarar 1902, Turawa suka kafa sabon lardin Zazzau. Keftin G.F Abadie ya zama Razdan na farko, Mista Daonisthorpe mataimakin Razdan a Wushishi.

Ko da yake ba a yi yaqi da Zariya ba, Turawa ba su huce fushinsu da Sarkin Zazzau Kwasau ba. Saboda suna zarginsa da mara wa Sarkin Kano Aliyu Babba baya wajen shirinsa na yaqi da Turawa. Sannan kuma ga shi ba su kama Magaji Xan Yamusa ba, wanda suke nema kamar ruwa a jallo. Saboda haka sai suka tsige Kwasau daga mulki suka mai da shi Lakwaja.[2] Aka danqa masarautar Zazzau ga Galadima Salmanu riqo kafin su ci Kano da Sakkwato da yaqi su naxa sabon Sarki. Da Turawa suka cimma muradinsu sai, Gwamna Lugga ya naxa Malam Aliyu Xan Sidi sabon Sarkin Zazzau. A ranar da za a naxa shi, Gwamna Lugga da hannunsa ya miqa masa riga da rawani.[3] A watan Yuli na shekarar 1904 aka cire Galadima Salmanu don ance yana son ya ja da sabon Sarki.

Wannan sabon naxin sai ya zo da wasu sauye-sauye da Turawan Mulki suka kawo. Lardin Zazzau ya fi kowane lardi girma a Arewa, sai aka rage masa faxi. Banda wannan kuma yana da yanki babba a Yamma wanda yake da qabilar Gbagyi, ana mulkinsu ta qarqashin garuruwan Birnin Gwari da Wushishi ko Kwongoma. Shugabanninsu kuma na zaune a waxannan garuruwa, suna kuma da matsayin Sarakuna masu daraja ta biyu. A shekarar 1908, sai Turawan mulki suka nemi su raba hanta da jini. Da suka yanke Yammacin lardin daga Zariya suka mai da shi zuwa lardin Nupe.[4] A wannan sauyi sai aka maida qabilun Gbagyi lardin Neja.

Tun kafin haka kuwa, a cikin shekarar 1907 an raba masarautar Zazzau zuwa gundumomi talatin da biyu. Amma bayan shekaru bakwai da yanke garuruwan qabilar Gbagyi aka maida su lardin Nupe a shekarar 1914, sai aka dawo mata da wasu gundumomi guda uku wato Jere da Janjalla da Kagarko. Da an fitar da su ne

---

1 *Zariya Provincial Gazetteer*, shafi na 14.

2 *Ibid*.

3 Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Arewa*, shafi na 77.

4 *Provincial Gazetteer*, shafi na 14.

daga lardin Nasarawa amma a waxannan sauye-sauyen sai aka maida su ga lardin zazzau.[1] Daga bisani sai sai aka haxe gundumar Janjalla da ta Jere.

Haka dai aka riqa yankar wannan vangare a liqa zuwa wancan vangare a wannan lardi mai faxin qasa, cike da jama'a da arziqin ma'adinai. A shekarar 1902, an shata iyakarsa ta Kudu da kogin Gurara kogin gulbi, shi ne lardin da ya yi iyaka da shi ta Yammaci. Saboda haka wannan sabon lardi na da faxin mirabba'in mil dube ashirin (20,000), an kuma qiyasce yana da yawan jama'a da suka kai yawan mutum dubu xari uku da hamsin (350, 000).[2]

A cikin shekarar 1902, Turawa sun rage faxin lardin Zazzau don su ladabtar da Sarkin Zazzau domin kashe wani Bature, mai suna Keftin Moloney da wani jarumin Sarki Kwasau ya yi a garin Keffi. Wannan jarumi mai suna Magaji Xan Yamusa, an ce ya yaqi Turawa vullar su Keffi ba tare da izinin Sarkin Zazzau Kwasau ba.

Magaji Xan Yamusa jarumi ne na inna-naha, an yi yaqe-yaqe da shi da yawa tun kafin vullowar Turawa, saboda haka yana xaya daga cikin manyan dakarun Zazzau a wannan lokaci. Ko da yake Magaji Xan Yamusa ba ya iya sarrafa hannayensa sosai, sai ya koma yana yaqi da qafafuwansa bisa kan doki kuma yana amfani da likkafar doki makamin yaqinsa. A fagen fama Magaji Xan Yamusa da likkafar dokinsa yake bai wa kura nama.

Turawa sun shiga garin Keffi qarqashin Keftin Moloney tare da mai tafintarsu, Audu Tuntun (Audu tafinta, saboda qibar da ya yi, shi ya sa ake masa laqabi da Tuntun). Jarumi Magaji Xan Yamusa sai ya gwabza da Turawa. An cewai Magaji Xan Yamusa da bindiga ya harbe Keftin Moloney sai ga bature rica kwance cikin jini. Daga nan sai yabi Tafinta Audun Tuntun har bakin kasuwa nan ya bar shi kolo na shan jininsa, da likkafar dokinsa ya kashe shi.[3] Dabarar yaqi irin ta Magaji Xan Yamusa daban take, domin idan ya zaburo bisa doki, kai kana tsammani zai kawo sara da takobi ko kuma suka da mashi ne, amma ina! Kafin ka yi aune sai ka ji likkafa mai kaifi a cikinka domin kuwa qafa zai miqo maka daga kan dokinsa.

Kashe Keftin Moloney ya tayar wa da Turawa hankali sosai, domin sun nemi Magajin Keffi Xan Yamusa ruwa a jallo saboda wannan ta'annati da ya aikata. Ko da yake Sarki Kwasau ba shi da hannu a kashe wannan Bature, bai kuma goyi bayan wanda ya yi kisan ba, sai Turawa suka rage masa faxin qasarsa. Sun yanke lardin Binuwai daga cikin Zazzau, sai kogin Gurara ya zama sabon iyakar lardin Zazzau.

---

1 *Provincial Gazetteer*, shafi na 7.

2 *Ibid.*, shafi na 14. 26.

3 Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 11 ga watan Satumba, 1984.

A shekararar 1907, an raba Lardin Zazzau zuwa gundumomi kashi talatin da biyu, kowanne na qarqashin mulkin Hakimi. Ga kadan daga cikinsu:

Igabi na qarqashin sarautar Turaki Babba
Giwa na qarqashin sarautar Fagaci
Jaji na qarqashin surautar Wombai
Kangiwa na qarqashin sarautar Iyan Gari
Kujama na qarqashin sarautar Wan'ya
Maqera na qarqashin sarautar Magaji Sambo
Zangon Katab na qarqashin sarautar Katuka
Kudaru na qarqashin sarautar Turaki Karami
Zangon Ayana qarqashin sarautar Xan Madami, da dai sauransu.[1]

Lardin Zazzau sai ya zama mai faxin murabba'in mil dubu ashirin da biyu (22,000 miles) ya miqa Yamma har wajen kogin Gulbi (wanda ya iya kance shi da lardin Kwantagora) ya kuma qunshi garuruwan Gbagyi da Wushishi. Har ila yau, a cikin shekarar 1908 an sake yanke wa lardin Zazzau faxin qasa. An yanke mata qasa mai faxin murabba'in mil dubu goma (10,000 miles) da ke Yammacin Zariya. Wannan qasar ta qunshi qabilar Gbagyi da sauran qabilun wajen, an maida su zuwa lardin Neja. Da garuruwan Minna da Bida da Abuja da sauran garuruwan da suke kusa da su, duk suna cikin lardin Zazzau ne.[2]

Saboda haka lardin Zazzau da ke da makeken girma, sai ga shi an tauye shi zuwa lardi mai faxin murabba'in mil dubu goma sha-uku da xari uku da ashirin (13,320 miles). Wannan sabon lardi yana iyaka da lardin Kano daga Arewa, daga Gabas yana iyaka da lardunan Bauci da Kano, daga Yamma kuma yana iyaka da lardunan Sakkwato da Neja, sannan daga Kudu yana iyaka da lardin Nasarawa. Allah Ya azurta wannan lardi da qabilu iri-iri, qasa mai albarka, da manya-manyan itatuwa, da tsibirai da manya-manyan koguna da rafuka. A cikin wannan lardi, akwai manyan koguna guda biyu, kogin Kaduna da kogin Gurara.

Kogin Kaduna

Babban kogin lardin Zazzau, shi ne kogin Kaduna. Shi wannan kogi ya faro daga tsaunukan Ganawari da ke lardin Bauci, sannan ya shigo cikin lardin Zazzau ta Kudu maso-Gabas, yana kaxawa Arewa zuwa Yamma har tsakiyar garin Girku, inda ya canja kaxawa daga Kudu zuwa Yamma har cikin lardin Neja a inda ya

---

[1] E. O. Oyedele, *Colonial Urbanisation: Kaduna*, shafi na 249

[2] *Provincial Gazetteer*, shafi na 5

haxe da kogin Neja wato kogin kwara.[1] Allah Ya albarkaci wannan makeken kogi da Kaduna wato "crocodiles " masu ximbin yawa, saboda haka ne ake yi masa laqabi da kogin Kaduna (River of Crocodiles), yana da wannan laqabi shekaru aru-aru kafin zuwan Turawa.

A zamanin da, idan 'yan fataucin shanu za su haye kogin sai su kan yi wata al'ada wadda za ta rufe bakin Kadunan ruf. Da yin wannan al'ada sai su zuba a kogin, sai kadoji su kasa buxe bakinsu sannan sai fataken su sa shanunsu ciki su yi iyo su haye. Ko da kada ya kawo bara ga saniya lokacin da take iyo, ba zai iya buxe bakinsa ba. Idan fataken suka haye kogin tare da shannunsu, sai su sake yin wata al'ada su zuba a cikin kogin wadda za ta buxe bakin Kadunan. Da yin haka sai ka ga bakin Kadunan ya buxe.[2] Saboda albarkar wannan kogi, garuruwa masu yawa sun kafu a gavarsa.

Makeken kogin nan na Kaduna na da isasshen ruwa, rani da damina, sa'an nan kuma cike yake da manya-manyan kifaye a inda mazauna gavar kogin suke yin sana'ar su. Albarkar qasa da yanayi mai kyau, ya sa qabilu daban-daban barin garuruwansu zuwa gavar wannan kogi mai albarka. Akwai garuruwa masu yawa da ke kusa da wannan kogi amma za mu kawo muku kaxan daga cikinsu, waxanda kuma ke da maqwabtaka da dajin Doka, dajin da Turawa suka kafa wani Sabon Gari mai suna 'Kaduna'.

A cikin waxannan garuruwa, akwai masu nisan zamani waxanda suka kafa biranensu, suke sha'anin mulki da, kasuwanci da yaqe-yaqe shekaru aru-aru kafin vullowar Nasara. Kafuwar waxannan garuruwa, bunqasarsu da dangantakarsu da juna zai wayar da kan jama'a matuqa wajen fahimtar zaman ka-zo-na-zo da Gbagyi, da Fulani, da Hausawa da Barebari suka yi a wannan wuri mai albarka kafin zuwan Turawa. Yin haka zai fahimtar da jama'a inda aka kafa garin Kaduna, da garuruwan da suke maqwabtaka da dajin da aka kafa garin. Wannan ya zama jazaman a wannan lokaci da jama'a ke zaton, wai an tashi garin wata qabila don kafa garin Kaduna. Za a fara da garin Afaka saboda matsayinsa na tushen mulkin garuruwan da ke gavar kogi da sauran garuruwa, da suka yi zamani a qarqashinsa.

Garin Afaka

Garin Afaka shi ne mafi girma, wanda kuma yana xaya daga cikin tsofaffin garuruwa ba ma a cikin lardin Zazzau ba, har a duk qasashen Hausa baqi xaya. A lokacin da garin ke tashensa, ya mallaki qasa mai faxi wadda ta qunshi shiyyar kogin Kaduna baki xayanta da sauran wurare kusa da nesa da kogin.

Mazaunan farko a wannan gari, su ne Hausawan Afaka. Shi wannan tsohon gari yana da nisan zamani matuqar gaske. Ana jin mazaunan farko sun fara

---

[1] E. O. Oyedele, *Colonial Urbanisation: Kaduna*, shafi na 249*Ibid*.

[2] Hira da Malam Tanimu Zariya, ran 12 ga Satumba 1984.

zamaninsu tun cikin qarshen qarni na takwas na Miladiyya. A cikin wannan qarni ne, wai aka yi wasu maharba da ke zaune a wani qauye mai suna Katai. Su waxannan maharban Katai ba a san haqiqanin daga inda suka fito ba, waxansu sun cewai daga garin Turunku suka fito, wai su ne mafitowar farko daga wannan gari. Garin Turunku ma wai Turkawa (Turks) mutanen "Turkey " ne suka kafa shi shekaru aru-aru da suka wuce, saboda haka ne ma aka sa wa garin sunansu wato Turunku ko kuma Turkawa. Kamar yadda ake cewa asalin mutanen Borgu daga qasar Farisa wato Iran suka taso.[1]

Wata rana waxansu maharba daga Katai sun fito yawon harbi sai suka hangi waxansu zabi, suka biyo zabin har suka yiwo Gabas da qauyensu zuwa wani kurmi. Da zuwan zabin nan wannan kurmi sai suka vacewa maharban nan, domin sun neme su sama da qasa ba su gan su ba. Wato dai su waxannan zabi sun 'fake' a wannan kurmi.

Ganin zabin da waxannan maharba suka biyo sun sami 'Mafaka' a wannan kurmi, sai maharban suka koma gida suka kwaso kayayyakinsu, suka dawo wannan kurmi da ke Gabas da qauyensu, suka kafa bukkoki suka zauna. A hankali sai jama'a suka riqa tasowa daga Katai suna zama a wannan sabon wuri, sai gari ya tashi bunqasa. Sai aka sanya wa wannan sabon gari suna 'Afaka' saboda mafakar da zabin nan suka samu a wannan kurmi inda sabon gari ya tashi.[2]

Cikin hanzari sai garin Afaka ya bunqasa sosai. Sana'ar mutanen garin noma da farauta. Addininsu ba zai wuce na al'ada ba, saboda musulunci bai vullo ba a wannan lokaci. Mazauna wannan gari na alfahari da cewa garinsu (Afaka) ya girme wa biranen Kano da Zariya, domin lokacin da garin ke tashensa ba a kafa waxannan birane ba. Su kan nuna wurare daban-daban na tarihi domin jaddada tsufan garin Afaka.

Duk da haka, garin na Afaka ba zai girme wa Kano zamanin Barbushe da Tsumburbura ba, waxanda ake jin sun yi zamaninsu a Dutsen Dala tun wajen qarni na Tara. Mai yiwuwa ne ma lokacin da Barbushe da Tsumburbura ke mulkinsu, garin Afaka ma na nasa havakar. To, amma idan haka ta auku, yaya garin Afaka bai fito cikin tarihi kamar Kano ba? Wata qila rashin samun albarkar qasa da jama'a irin ta Kano da kuma rashin gogaggun mutane waxanda za su fitar da sunan garinsu duniya ta san shi, sun dakushe garin Afaka matuqar gaske har ya zamana bai fito fili ba. Haka kuma mutanen wannan gari ba su cika son baqi su zo zama a wannan gari ba. Alal misali, da wani mashahurin malami Bafilatani mai suna malam Dabo ya taso daga garin Gulu ta qasar Nupe, an ce ya yada zango a

---

[1] Jakadan Qasar Iran a Nijeriya, Mr. Torkobadi ya bani wannan larabi a Abuja a shekarar 2005. Har ma ya ce mutanen Borgu sun ba shi wata sarauta.

[2] Hira da Sarkin Afaka Alhaji Umaru ran 7 ga Satumba 1984.

garin Afaka, inda har ya gina masallaci. Amma sai shugabannin gari suka roqe shi da ya bar garinsu saboda suna tsoron zai shahara ya mallake garinsu.

A zamanin da garin Afaka yake tashe, faxin garin da tsawonsa kusan mil bibbiyu ne, kuma cike yake da jama'a. Tsofaffi na raxe-raxin cewa sai da garin Afaka ya samu misalin shekaru xari uku ba a sami garin da ya ci shi da yaqi ba. Ko da yake jama'ar wannan gari an ce sun fito sun kafa garuruwa da dama, amma babu wasu muhimman garuruwa da aka ce garin Afaka ya ci da yaqi.

Babban dalilin tauyewar wannan tsohon gari shi ne annobar ciwo. Annobar cutuka iri-iri sun tauye havakar wannan gari qwarai da gaske. An ce an yi wata mummunar annobar ciwon mai baushe cikin qarni na goma sha-takwas wadda ta kusa hallaka jama'ar garin baqi xaya. Wannan annoba wadda ita ce kusan ta qarshe ta ragargaza garin baki xaya har ma 'yan tsirarun jama'ar da suka ragu su ne suke ta ci gaba da hayayyafa, garin kuma ya dawo xan qaramin qauye. Allahu Akbar! Allah Shi ne Mai xaukaka garin da Ya so, Ya kuma tauye garin da Ya so domin Shi ne mai ximbin iko!

Inda tarihin garin Afaka ya bambanta da sauran tsofaffin garuruwan lardin Zazzau, shi ne tsofaffi na bayar da labarin cewa a inda aka kafa wannan gari da kewayensa har ya zuwa bakin kogin Kaduna, a nan ne wai aka yi babban birnin Darmasilu. A wannan birni ne Fir'auna ya yi zamaninsa fiye da shekaru dubu huxu da suka wuce. Mazauna garin Afaka su kan nuna wuraren tarihi masu yawa don jaddada abin da tsofaffi ke faxi game da garin nasu.[1]

Irin wannan labari ba sabon abu ba ne a qasashen Hausa. Tsofaffi na bayar da irin wannan labari mai nuna an yi wasu alqaryu a zamani mai nisa a sassa daban-daban a wannan qasa. Misali, a kan ce Adawa ko kuma Samudawa sun yi zamani a wajen qasar Sakkwato, har su kan nuna wasu manyan tuloluwar qasa da su kan cewai Kaburburan irin waxannan mutane ne (a qauyen Dutsi da ke cikin Zurmi). Wani bincike da wani masani Bature, mai suna R. Soper ya yi a wasu sassa na qasar Zamfara, ya gano abubuwa da dama da ake tsammani mutum ya yi amfani da su a zamanin Dutse wato (Stone age). An qiyasta cewa an yi su ne da dutse. An qiyasta cewa wasu daga cikin waxannan abubuwa tsufansu ya kai shekaru dubu arba'in. Wani abin sha'awa shi ne, qauyen Dutsi da tsofaffi ke ba da labarin cewa akwai Kaburburan Adawa, akwai wani wuri kilomita arba'in ne kawai daga inda R. Soper ya gano wasu kayan Dutse a kan kogin Gagare.[2] Ka ga a nan labaran da tsofaffi kan bayar lallai wata hujja ce mai qarfi da ke nuna cewa xan-Adam ya yi zama a sassa masu yawa a cikin qasar Hausa shekaru masu nisan gaske da suka wuce.

---

[1] Hira da Sarkin Afaka Alhaji Umaru da wasu dattatawa, a tsohon garin Afaka a ran 7 ga Satumba 1984.

[2] Mujallar Tarihi ta Jihar Sakkwato, shafi na 29

Tarihin Manyan daulolin da aka yi can da bai shige qarni na goma sha-biyar ba, wato dai ba su shige shekaru xari huxu ko xari biyar da suka wuce ba. Amma abin lura shi ne cewa tun lokaci mai tsawo kafin wannan qarni na goma sha-biyar, mutane sun yi zamani a wurare masu yawa cikin qasar Hausa. Hasali ma, da yake tarihin kowace jama'a abu ne haxaxxe tun farkonsa har zuwa yanzu, wato ba mai tsinkewa ne ba, muddin dai ba jama'ar ta hallaka gaba xaya ba. Wannan dalili, shi ya sa tsofaffi ke ba da labari iri-iri na tarihin qasashensu ga 'ya'yansu. Ko da yake ba su iya tuna komai da komai, amma duk da haka abin da ake samu a wajensu madogara cewajen rubutun tarihi.

Amma duk da haka a halin yanzu, akwai hanyoyi da dama waxanda masana tarihi ke bi suna gane yadda rayuwar xan-Adam ta kasance a wannan zamani. Waxannan hanyoyi sun haxa da tono abubuwa da suka shafi mutum a wannan lokaci, a kuma yi nazari kansu wato ta tarihin qarqashin qasa *Archaeology*, da bincike a kan wasu halayen rayuwar jama'a a halin da muke ciki, amma waxanda yake akwai alamun cewa tun shekaru aru-aru ake yinsu wato *Ethnography* da yin bincike a kan harsunansu wato *Linguistics*, wani lokaci har ma da binciken yanayin qasarsu da tsire-tsirenta da kuma shuke-shukensu. Masana su kan yi qoqari su tattara abubuwan da suke iya ganewa daga dukkan waxannan fannoni da kuma irin labarun da suka rage, su yi nazarinsu, sa'an nan su fayyace tarihin jama'ar sosai.

Wajen garin Afaka kuwa, babu wani babban bincike da aka yi, amma akwai wurare masu yawa da suke nuna alamun xan-Adam ya yi zamani mai tsawo a wannan wuri. Misali, akwai wata rijiya da aka cewai rijiyar Fir'auna ce da sawun mutum kan wani dutse da sauran abubuwan tarihi. Qabilun Gbagyi da Fulani su ne baqin farko da suka fara shigowa cikin qasar Afaka, inda suka kafa qauyukansu a sassa da dama.

Vullowar Qabilar Gbagyi

Akwai qabilu iri-iri a Yammaci da kudancin lardin Zazzau. Qabilar Gbagyi na da dangantaka da vangaren ko sashin kogin Kaduna domin tun safiyar fari suka vullo zuwa wurin, suka zauna a 'yan qauyuka masu dama a qasar Afaka.

An cewai qabilar Gbagyi su ne mazaunan farko a qasar Barno, sun bar qasar ta Barno saboda juyin Islama, inda suka watsu zuwa qasashe kamar su Katsina, Zariya da Birnin-Gwari. A wani qaulin kuma an ce Gbagyi sun tafi Abuja bayan da Sarkin Zazzau ya kafata. Shi Abuja xan Sarkin Zazzau Muhammadu Makau ne, wanda Fulani suka kora daga Zariya a lokacin Jihadin Shehu Mujaddadi Usman. Shi Abuja mutum ne mai tsawon qafa biyar da rabi (5' 6) kakkaura ne kuma jawur. Saboda jansa ne ake ce masa 'Jatau', wani lokaci kuma ana yi masa laqabi da "Abuja " wato "Abu-jawur. " Shi Allah Ya yi shi jarumi ne, don haka ne

ake masa kirari da "Jatau Shugaban Gari mai ganuwa ko fagen fama kai ke fara fitar da jini. "

Abuja ya kafa garin da ya sa wa sunansa Abuja ranar Lahadi, goma ga watan Sha'aban 1825. Gbagyi sun tafi sun zauna can garin Abuja. A wannan wuri inda Sarkin Zazzau na 62, wato a Sarautar Have akwai qabilu masu yawa, kamar Gbagyin Genge da Gbagyin Yamma da qabilar Koro da Gade da Ganagana da 'yan tsirarun qabilar Gwandara da Bassa da kuma Fulani.

A lardin Neja ne qabilar Gbagyi ta fi yawo ta fi kuma samun gindin zama tun da wannan qabilar ta vullo daga qasar Barno a shekaru aru-aru da suka wuce. A wannan lardin Neja, qabilar Gbagyi na da mazaunai masu yawa a kuma wurare daban-daban. Ana samun su a Kuta, da Galadiman-Kogo, da Fuka, da Guni, da Gini, da Sarkin Pawa, da Dangunu, da Allawa, da Bosso, da Erena, da Maikunkele, da Minna, da Manta, da Gussoro da Paiko.[1]

Qabilar Gbagyi ta watsu a sassa daban-daban a tsakiyar yankin qasar nan wato *Middle Belt*. Asalin Gbagyi sun fito ne daga qasar Barno. Daga nan ne suka watsu zuwa wurare masu yawa. Ko da yake suna da al'adu kusan xaya amma sun kasu kashi biyu. Gbagyin da suke maqwabtaka da Hausa a Arewa, Hausawa na yi masu laqabi da Gbagyin Yamma, waxanda suke Arewa maso-Gabas kuwa ana kiran su Gbagyin Genge. Hausawa ne suka banbanta su saboda bambancin inda suke zaune, amma ba na al'adu ba. Duk da haka akwai, 'yan bambance – bambancewajen harshe da xabi'u.[2]

Ko da yake qabilar Gbagyi sun fi sauran qabilu yawa, amma sai qabilar Koro suka danne su. A wannan zamani, lokaci ne na yaqe-yaqe tsakanin qabilu domin mallakar qasa. Gbagyi ba su tavuka komai ba wajen mallakar qasar kansu, a wannan waje sai suka tashi a tutar babu domin ba su da qasar kansu. Saboda rashin mallakar qasar kansu ne, sai suka zo daga baya bayan qura ta lafa, suna masu neman iznin zama ba domin nuna fifikon qarfi ba. duniya a tsaye take, a wannan lokaci mallakar qasa sai da qarfin tuwo. Wannan dalili shi ya sa sai ka gan su a qasa wadda ba mallakinsu ba, wadda kuma a kowace shekara sai sun biya harajin qasa. Idan ba a ba su iznin zama ba, sai su kan tattara inasu-inasu su yi gaba.

Saboda yawan qabilar Gbagyi a lardin Abuja da kuma rashin samun qasar kansu, sai a hankali suka watsu, galibinsu suka yiwo cikin qasar Afaka suka kafa garuruwa da dama. A kowace shekara sai su kai harajin qasa ga Afaka. Tarihi ya nuna ko a can lardin Neja yankin da ke qarqashin Zazzau kafin shekarar 1908,

---

1 NAK SNP 17-52006/1911 *Map on Kuta Division, Niger-Province* 1911.

2 Isa Nanbo Baba, *The Evolution of the States Systems Among the Gbagyi of River Kaduna Valley* C. 1860 to 1981, PhD Thesis April, 2006, shafi na 25

qabilar Gbagyi ba su mallaki qasar kansu ba, amma suna da garuruwa a wurare masu yawa a cikin wannan lardi.

A wani qaulin kuma, an ce Gbagyin da ke zaune a gavar kogin Kaduna, Gbagyin Yamma ne, wato 'Gbagyi Wyi'. Su waxannan qabilu sun fito daga Birnin-Gwari, asalinsu Gbagyin Kuta-Fika ne, waxanda suka zo daga qasar Borno inda suka zauna a Kuta a cikin shekarar 1600 A.D. Daga nan ne suka watsu wurare masu yawa suka kafa qauyuka da garuruwa har da Kakuri.

Kakuri Kurmin Gwari

An kafa wannan gari a zamanin da Nagwamatse ya koro Gbagyi daga yankin Neja, saboda haka sai suka samu wannan wuri da ke kurmi, wato (forest), suka kafa wata tunga. Daga nan sai ana kiran wurin Kurmin Gwari, saboda suna zaune a wannan Kurmi ne. Wannan ya faru ne musamman a lokacin Ibrahim Nagwamatse, wanda ya yi qaurin suna wajen yaqi da hare-haren kama bayi. A kan haka ne, C.R. Niven ya ce: "Ya yi ta harin qasar Gwari sau da yawa, ya kashe mutanenta da yawa, dalili ke nan har yanzu qasar ba ta da jama'a da yawa. "[1] Wata qila, a wannan lokaci ne da yawa daga cikinsu suka samu mafaka a wannan kurmi, inda suka zama maqwabtan Fulani a Barnawa. In bazara ta yi sai su zo su samu wurin noma a wurin Sarakunan Barnawa, in rani kuma ya yi lokacin da mayaqa ke kawo hari sai su koma cikin kurminsu. Tun da aka tarwatsa su a lokacin hare-haren kamun bayi, ba kasafai suke shiga jama'a ba. Ba su kuma son su fito fili su kafa gari ba. Wato wannan yanki ya samu baqin qabilar Gbagyi daga yankin Neja. Sun watsu har cikin qasar Afaka. Haka ake zaune tsawon zamani har zuwan Turawa.[2]

Wannan gari kamar yadda ake kiransa, babban kurmi ne mai wuyar shiga saboda sagagi da manyan itatuwa da suka kewaye garin, har hanyar shiga garin ma sai wanda ya sani. Ana zama a kurmi saboda qarin tsaro daga mahara, kamar yadda ake gina ganuwa a garuruwa. Babu takamaiman lokacin da aka kafa wannan gari, amma ana jin gari ne na gargajiya wanda ake jin ya kafu tun cikin farkon shekarar 1600 A.D. Gbagyin Kuta ne suka kafa wannan gari a bakin gavar kogin Kaduna. Saboda haka ake jin cewa Gbagyi 'yan asalin qasar Barno ne, sun shigo qasar Afaka tun kafin yaqe-yaqen Nagwamatse. Amma sun qara kwararowa ne zuwa qasar Afaka a lokacin yaqe-yakensa.

Duk garuruwan Gbagyi da ke gavar kogin Kaduna babu kamar wannan gari. Tun fil-azal, shi ne mahaxar Gbagyi da suka shigo qasar Afaka, domin a wannan gari ne suke taruwa don shawarwari. Ko da yake ana cewa waxannan qabilu ba su

---

[1] C.R Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na 35.

[2] Alhaji Zubairu Hakimin Barnawa, *Kundin Tarihin Barnawa*

da shugabanni, amma Gbagyi mazauna qasar Afaka suna da 'yan garuruwa kuma da shugabanni, don haka ne Kakuri ta zama kamar hedkwatarsu.

An ce sun yi wani shugaba ana kiransa Kakura, a zamaninsa ne aka tara leburorin fasa dutse a Arewa da Kurmin Gbagyi har wurin ya zama matattarar Hausawa, inda fatake su kan yi zango a wannan wuri. Hasali ma dai Sarakunan Zazzau masu karvo haraji daga qasar Nupe zuwa Zariya su kan sauka a wannan wuri. A dalilin haka ne aka samu sabon mazaunin jama'a a kusa da kurmin Gwari. Saboda haka sai aka sa sunan unguwanni guda biyu, xaya Kakuri Gbagyi, xaya kuma Kakuri Hausa. A Kakuri Gbagyi da ma suna da shugabansu mai suna Kakura. Bayan mutuwarsa aka naxa masu wani mai suna Angulu, shi wannan Sarkin Kakuri Gbagyi ya zama Musulmi daga baya a bayan lokacin rasuwarsa sai Gwarawa suka rufe shi, amma sai Musulmi suka tone shi, don su yi ma shi jana'iza irin ta musulunci. Bayan Angulu sai Sarkin Kakuri Gwari Malam Sale wanda aka naxa Sarkin Kakuri Gbagyi.[1] Wata qila wannan gari ya samo sunansa ne daga Sarki Kakura. A zamaninsa sai garin ya zama "Kakuri. "

Su Gbagyin amana ne don haka kowace shekara suna kai murgu wato (haraji) zuwa garin Afaka. Mazauna wannan gari sana'arsu dai noma, da farauta da kamun-kifi saboda tafkeken kogin Kaduna da ke kusa da su. Wajen noma, waxannan qabilu na da qoqari sosai, su kan yi noman kayayyakin abinci iri-iri waxanda suke sayar wa sauran a maqwabtansu. Halayyar aikin gonakinsu daban take da ta sauran qabilu. Da zarar damina ta gabato, sai Gbagyi su shiga gyara gidajen gonakinsu. Su kan yi gonakinsu nesa da garinsu, don haka ne suke gina 'yan gidajen gona. Vullowar damina ke da wuya sai ka ga duk gidajen gonakinsu sun gyara, sun kuma shiga aikin noma tuquru.

Da damina ta tsaya sai duk samari da 'yan mata da dattawa su kwashi kayayyakin aikin gona, kayan abinci da sauransu domin kaiwa da tarewa a gidan gona. Waxanda ake bari a gida sai mata masu yara qanana da tsofaffi, ko marasa lafiya. A kan bar mazaje masu tsaron gari. Saboda haka lokacin aikin gona ba ka samun kowa a gari duk sun duqufa wajen aikin gona. Ba za su dawo gida ba sai duk sun kammala aikin gona, an yi shuka da noma kuma yabanya ta yi kyau kafin a dawo gida. Yin haka ya rage zirga-zirga tsakanin gida da gona. Ba za su koma gidajen gonakinsu ba sai lokacin girbi, amma za su riqa kewaya gonakinsu a lokaci-lokaci har lokacin girbi.

Zaman gona yana cike da haxurra daban-daban ban da farmakin mahara waxanda suke Hausawan garin Afaka ne, akwai fama da namun jeji. Saboda haka Gbagyi su kan xauki matakai iri-iri wajen kare kawunansu. Kafa gari cikin kurmi yana karesu daga sharrin mahara. Su kan yi wa juna saqo ta busa sArewa a

[1] Alhaji Zubairu Hakimin Barnawa, *Kundin Tarihin Barnawa*

wannan zamani. Akwai salon busa sArewa iri-iri, idan ka ji an rera sArewar da ke nuna akwai haxari tafe, sai ka himmatu ka san inda dare ya yi maka.

Idan kaka ta yi, kuma an samu albarkacin noma, matan Gbagyi na kai kayayyakinsu kasuwannin garuruwan da suke maqwabtaka da su. Kamar Kangiwa, Maqera da Barnawa. Allah Ya yi matan Gbagyi qarfafa, ga su kuma da jimirin aiki. Ban da kayayyakin gona, su kan kai tallar itace, waxanda maqwabtansu kan saya domin girki. Ba su cika son xaukar kaya a ka ba, kamar sauran qabilu, komai nauyin kaya su kan xora shi bisa doron bayansu.

Kakuri gari ne babba wanda yake da qauyukan Gbagyi da yawa qarqashinsa. Shugabannin wasu qauyukan Gbagyi a Kakuri ake naxa su. Saboda wannan girma, Gbagyin wannan kurmi tun tuni suke da shugabanni. Akwai shugabanni da dama waxanda suka yi zamani shekaru aru-aru da suka wuce. Shugaban da Turawa suka tarar yana mulki a Kurmin Gbagyi, shi ne Sarkin Gbagyi Jagaba. A lokacin mulkinsa ne hanyar jirgin-Baro zuwa Kano ta kawo bakin kogin Kaduna. Bayan shugabancin Jagaba, sai shugabancin Gbagyi ya koma hannun Mizauna.[1]

Kakuri Hausa

Saboda zuwan Turawa da ma'aikatan hanyar jirgi da kuma tashar jirgi (Kaduna South) da aka yi a Kakuri, garin ya havaka sosai cikin hanzari. Duk kurmin da ke kewaye da garin, sai da aka sassabe su garin ya fito fili, alqarya ta ci gaba da havaka. Nan da nan sai ga garin Kakuri da Maqera na cika da jama'a ma'aikata, leburori da sojoji.

Wannan gari ya kafu ne a lokacin da Arewacin Kaduna ke samun qaruwar jama'a daga sassa daban-daban na Nijeriya, saboda havakar tashar jirgin qasa a wannan yanki. Wanda ya fara zama Sarki a wannan sabuwar unguwa, wani BaKano mutumin Haxeja ne mai suna Malam Mudi. Bayan rasuwarsa sai aka naxa wani Bafilatanin Barnawa, mai suna Malam Adamu. Shi Adamu bayan an tuve shi daga sarautar Kakuri Hausa sai ya koma Nasarawa inda aka naxa shi Sarkin Nasarawa. Bayan rasuwarsa aka naxa xan shi Sarkin Nasarawa. Zuriyarsa ke sarautar wannan gari zuwa yanzu. Bayan tuve Malam Adamu daga sarautar Kakuri Hausa sai aka naxa Ahmadu xan Kabo Sarkin Kakuri Hausa. Bayan rasuwarsa aka naxa xansa Musa Ahmadu. Duk waxannan naxe-naxe ana yin su ne da izinin Mai martaba Sarkin Zazzau, domin duk waxannan wurare a qarqashin qasar Zazzau suke. Sarakunan Zazzau sun sa ido sosai a sha'anin mulkinsa, musamman a zuwan Turawa.[2]

Vullowar Gbagyi qasar Afaka ke da wuya, sai suka shiga zaman "Mai akuyana roqon Allah, mai kura na roqon Allah! " wato zaman doya da manja, ko

---

[1] Hira da Jagaba Sarkin Kakuri Kurmin Gwari, ran 15 ga Satumba 1984.

[2] Alhaji Kabiru Zubairu, *Kundin Tarihin Barnawa*.

da yake Gbagyi mutane ne masu son zaman lafiya, kuma sun zo suna zaune a bisa amana, amma sai aka wayi gari zaman lafiya ya yi kusan gagarar su. Kowace shekara sai sun kai murgu (haraji) ga Afaka.

Idan har suka makara ba su kai haraji ba, to, yanzu "Tuwa ya ci su. " Saboda haka sai dakaru su yi wo hawa daga garin Afaka, su bazamo su haye kogin Kaduna su shiga cikin Kakuri-Kurmin Gbagyi. Nan da nan sai su kame masu 'yan mata da samarin garin, su tafi da su kamar sun kama bayi, su kai su Afaka su tsare. Idan haka ta faru, to, "Tuwa " ya ci Gbagyin Kakuri ke nan. Dole iyayen matasan da aka kama su kai dabbobi da hatsi garin Afaka domin fansar 'ya'yansu.

Duk lokacin da Tuwa ya ci waxannan Gwarawa sai ka ga garin ya yi tajin-tajin, iyaye na ta kuka saboda raba su da 'ya'yansu da aka yi. Su kuma dattawa sai ka gan su cikin maye, maye wanda ba na giya ba, amma na baqin ciki. Haka dai za su qoqarta su samu dabbobi da hatsi su kai Afaka domin fanso 'ya'yansu.[1]

Duk garuruwan Gbagyi da ke qasar Afaka haka Tuwa ke cin su, kamar su; *Litore* da Kurmin Mashi da Kurmin Kudandan da Kakuri Kurmin Gwari. A kowane lokaci waxannan Gwarawa suna zaune cikin fargabar hari. Wani lokaci ma ana yi wo hawa takanas domin a zalunce su, ba don sun makara wajen kai haraji ba.

Irin wannan zalunci da muzgunawa da mulkin danniya da Hausawan Afaka ke nuna wa Gwarawa, shi ya hana zaman lumana tsakaninsu, wannan shi ya sa Gbagyi zama cikin Kurmi. Saboda sanin halayyar zaluncin Hausawan-Afaka shi ya hana Gwarawa zama kusa da su sosai. Matuqar Gwarawa suka ji motsin Hausawa kusa da su sai su tashi su lula can nesa domin nema wa kansu sa'ida. Wannan ya sa jama'a ke cewa wai Gwarawa ba sa son zama cikin mutane. Haka dai waxannan qabilu suke zaman 'mai akuyana roqon-Allah, mai kura shi ma yana roqon Allah', har vullowar Fulani.

Vullowar Fulani

Isasshen ruwan sama da qasa mai albarka da tafkeken kogin Kaduna, sun janyo hankalin Fulani masu kiwo zuwa wannan wuri, shekaru masu yawa da suka wuce. An cewai Fulani sun shigo wannan lardi na Zazzau don neman wajen kiwon shanu. Gavar kogin Kaduna ta ba su sha'awa qwarai da gaske. Saboda sun ga ciyayi koraye shar, rani da damina.

Rukunin Fulani na farko, sun kafa ruga a wani wuri dab da bakin kogi, Gabas da Kakuri-Kurmin Gbagyi. Kamar Kakuri, babu wani haqiqanin lokacin da suka zo suka kafa wannan ruga, amma ana jin dab da kafuwar Kakuri ne. Wannan rugar Fulani ita ma ta jima da zamani, domin tsofaffi na raxe-raxin cewa mai

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim, a ran 15 ga Nuwamba 1984.

yiwuwa ta girme wa Zariya. Wannan rugar ta Fulani ita ce ta zama garin Barnawa daga baya.[1] Tsofaffi masu ba da labari sun bambanta wannan wuri, a wani qauli kuma an ce Fulani sun riga Gbagyi shigowa qasar Afaka. Wasu kuma suna jin Gwarawa ne suka fara vullowa wannan wuri. To, koma wa ya riga wani, dukkansu dai zuwa suka yi tun asubahin fari.

Rukunin Fulani na biyu, sun fito daga garin Bebeji ta qasar Kano, qarqashin wani Bafillatani mai suna Aliyu Magajin Jammu a cikin farkon qarni na goma sha-bakwai, ana jin lokacin da Ishaku ke sarautar Zazzau ne.

Aliyu Magajin Jammu ya baro Bebeji tare da iyalansa da barorinsa da garken shanunsa ya yiwo Kudu har zuwa wani wuri mai qaton dutse (kusa da tsohon filin jirgin saman Kaduna) da ke kusa da Afaka. A kusa da wannan babban dutse, sai Aliyu Magajin Jammu ya kafa garken shanunsa, sannan ya koma cikin garin Afaka da zama, ya kuma sa wa wannan sabon garken shanunsa suna 'Karina'.

'Ya'yansa da barorinsa sai suka shiga aikinsu na kiwo a Karina, sa'an nan kullum sai sun tatsi madara sun kai wa Maigidansu da ke zaune a garin Afaka. Cikin xan qaramin lokaci, sai arziqin Aliyu Magajin Jammu ya fara tashi sosai. Shanu, da awaki da tumaki sai hayayyafa suke yi. Karina kuma inda wannan Bafillatani ya kafa sai ya tasamma havaka sosai, sai jama'a ke zuwa suna zama, har alqarya ta fara kafuwa cikin hanzari.[2]

Tashin arziqin wannan Bafillatani ya tayar wa da Hausawan Afaka rai sosai, saboda haka sai suka shiga yin shawarwarin yadda za su fito wa wannan al'amari. Sai mutanen Afaka suka kai wa Sarkinsu labari da shawarwari cewa, ga wani baqon Bafillatani wanda ya zo kwanan nan, amma ga shi yana tashen arziqi, suka ci gaba da cewa Sarkinsu, matuqar bai kori wannan Bafillatani ba, to, wallahi wata rana za a wayi gari ya mallake masa qasarsa baki xaya.

Wanda ke sarautar Afaka a wannan lokaci shi ne, Sarkin Afaka Mai Babbar Hula. Shi wannan Sarki ana yi masa laqabi da Mai Babbar Hula ne domin idan ya sa wata hula tasa, to, kowane ne ya saurara masa. Idan ya ga dama yana iya yi wa garken shanun Bafillatanin tsawa, da yin hakan sai Bafillatanin ya nemi shanunsa sama da qasa ya rasa ganin su. Idan haka ta auku, sai Bafillatanin ya kawo goro sannan a ba shi iznin ganin shanunsa. Sarki Mai Babbar Hula ya shahara a zamaninsa sosai don kowa ya taka, to, ya taku ba a garinsa Afaka ba har da maqwabtansa.

Amma labarin da Sarkin ya samu game da Aliyu Magajin Jammu ya tayar masa da hankali qwarai da gaske, saboda haka sai ya kirawo wannan Bafillatani ya kuma umarce shi da ya bar masa garinsa, ya tafi duk inda yake so ya kafa gari

---

[1] *Kundin Tarihin Barnawa* na Alhaji Kabiru Zubairu.

[2] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim, ran 15 ga Nuwamba 1984. Yana Xaya daga cikin Zuriyar Aliyu Magajin Jammu.

a cikin qasar Afaka, amma dolensa ne ya bar garin a cikin hanzari. An cewai haka mutanen garin suka umurci malam Dabo da ya bar garinsu domin tsoron kada ya mallake masu gari. Da zuwan Malam Dabo wannan gari har ya gina masallaci. A masallaci ne wasu bayin Allah suka nemi mafaka a cikinsa a lokacin da Turawa suka vullo, saboda qyamar Turawa sai malaman suka shige, wannan masallaci suka roqi Allah da masallacin ya rufa da su, haka kuma aka yi.[1] Malam Dabo sai ya taho Zariya inda Sarkin Zazzau ya umurce shi da ya tafi Kano.

An ce kafin malam Dabo ya tafi Zariya sai da ya bi ta wani qauye da ake kira Kuyallo. A wannan qauye, Malam Dabo sai ya sauka a wani gida inda garunsu ya kusa ruftawa, saboda ruwa da damina. Wannan Mashahurin Malami sai ya ce da garun xakin da zai zauna, "tsaya! " Haka garun ya tsaya ya rusuna kamar zai rifta amma bai rifta ba. A wannan xakin ya yi ta ijtihadin roqon Allah, kafin ya tafi Zariya. Amma kafin wannan mashahurin malami ya tafi Zariya sai malaman fadar Sarki suka baiwa Sarkin Zazzau Abdullahi labarin zuwan wani baqon Bafilatanin malami qasarsa, suka kuma shaida masa cewa im bai yi hankali ba, to, za su ci abinci a akushi guda da wannan malami.

To, a kwana a tashi sai ga malam Dabo ya zo yana rataye da gafakar Alqur'ani, da buzun-salla da butar alwala ya iso birnin Zazzau. Idan ka ganshi ka ga malami mai muhibba kuma taqiyyi. Amma tun kafin zuwansa Sarkin Zazzau yasa an duqufa da roqon Allah da Ya kare mulkinsa don kada wannan baqo ya zo ya ci abinci da shi a akunshinsa wato ya karve mulqinsa!

Kwaram! Sai ga malam Dabo a fadar Zazzau yana neman a bashi masauki. Da ganinsa fa sai hankalin Sarki da malamansa suka tashi haiqan. Ai Sarki ne ke baiwa malami masauki. Saboda haka sai aka ba shi masaukin da ya dace da shi, aka kuma karrama shi kamar yadda ya dace. Amma kuma ana xar-xar da zuwansa fadar Zazzau.[2]

To, ana cikin wannan hali sai ga saqo daga fadar Sarkin Kano. Sarkin Kano Sulaiman na buqatar Sarkin Zazzau ya aiko masa da malami wanda zai naxa liman. Nan da nan sai Sarkin Zazzau ya ce da babban baqonsa cewa zai aika da shi Kano saboda a can ne abincinsa yake. Saboda haka sai aka aika da shi fadar Sarkin Kano. Malam Dabo ya zama qasaitaccen limamin birnin Kano. Shi ne kuma ya zama Sarkin Kano, zuriyarsa ke sarautar Kano har yanzu.[3]

To, idan muka dawo labarin Sarkin Afaka, sai muga kamar yadda aka yiwa malam Dabo haka aka yiwa malam Jammu. Sarkin Afaka ya umurce shi da ya

---

[1] Hira da Sarkin Afaka, Alhaji Umar ran 5 ga Disamba 1984. A lokacin ne ya nuna mani tarin Qasar Masallacin Malam Dabo, wanda ya zama kabarin wasu Malamai masu gudun Turawa. Saboda zuwansu alamar tashin Qiyama ce.

[2] Hira da Malam Tanimu Zariya. Ran 10 ga Disamba 1984.

[3] *Ibid*.

tashi ya bar garinsa. Samun wannan umarnin Sarki ke da wuya, sai Aliyu Magajin Jammu ya kwashe komatsansa da iyalansa da dabbobinsa ya shillo, ya yiwo Kudu da Afaka har ya zuwa gavar kogin Kaduna inda ya kafa Sabon Gari. Garin Karina da ya baro sai yaci gaba da girma a hankali.

Garin Kinkinau

Da Aliyu Magajin Jammu ya taso daga Afaka ya zo gavar kogin Kaduna sai wajen ya qayatar da shi domin kuwa akwai isasshen ruwa da ciyayi koraye shar. A wannan waje ne ya kafa Sabon Gari. Da zuwan Fulani wannan sabon wuri, sai Magajin Jammu ya ce, a sa wa wajen sunan baiwarsa Keke. Sai aka sa wa wannan sabon wuri 'Unguwar Keke.' Fulani suka manta da abin da Hausawan Afaka suka yi masu, suka ci gaba da hidimomin kiwo, a hankali sai sabon garin nasu ya tasamma girma.

Ko da yake korar da aka yi wa Aliyu Magajin Jammu daga Afaka, ta baqanta masa rai, amma ya nuna haquri, ya kuma dogara ga Allah, ya zauna a sabon garinsa, yaci gaba da sha'aninsa.

Amma Sarki Mai Babbar Hula ya yi nadama daga baya, bisa ga abin da ya yi wa wannan Bafillatani. Ai bai kamata kamarsa ya nuna hassada ga arziqin talakan qasarsa ba, ballantana in talakan ma baqo ne, wanda ya zo daga nisan duniya don neman arziqi. Fahimtar wannan aibi shi ya sa ya nemi matakin da zai bi don ya gyara danqon zumunci tsakaninsa da Aliyu Magajin Jammu, don haka sai ya ba shi kyautar dajin Doka.

Sarkin Afaka ya ce da Aliyu, "Allah Ya kawo ku wannan sabon wuri (wato Unguwar Keke), mai albarkar ruwa da ciyayi, saboda ka samu wuri isasshe don kiwo, na ba ka jejin da ke Gabas da wannan gari (wato Dajin Doka) " Aliyu Magajin Jammu ya yi godiya da kuma nuna farin cikinsa da wannan "Muhimmiyyar " kyauta da aka yi masa.[1]

Babu muhimmanci ga wannan kyauta da aka yi na dajin Doka a wannan lokaci, saboda dajin doka ba shi da kyawon kiwo, domin cike yake da manya-manyan itatuwan Doka da namun jeji iri-iri, musamman zakoki. Duk da haka wanda ya yi kyautar da wanda aka yi wa kyautar babu wanda ya fahimci muhimmancin wannan kyauta sai a zuwan Nasara (Turawa). A wannan daji ne ko kuma dajin Aliyu Magajin Jammu, Turawa suka kafa wani babban gari mai suna Kaduna.

Wannan abu da ya faru, abin al'ajabi ne kuma hikima ce ta Ubangiji Mabuwayin Sarki. An yi gudun gara an faxa zago, mutumin da aka kora daga garin Afaka saboda tsoron kada ya mallake garin, sai ga shi wanda ya yi korar ya

---

[1] Hira da Sarkin Afaka Alhaji Umaru da Sarkin Unguwar Shanu Alhaji Ibrahim, a Sabuwar Afaka. Ran 15 ga watan Disamba, 1984.

yi kyauta muhimmiya wadda muhimmancin kyautar sai bayan shekaru aru-aru ta fito. Garin da aka kafa a dajin Aliyu Magajin Jammu sai ga shi ya mallake duk sauran qananan garuruwa da manyan garuruwa ba na cikin lardin Zazzau ba ma duk lardunan Arewa baki xaya. Allahu Akbar! "Lallai Hassada ga mai rabo taki ne. "

Da Unguwar Keke ta havaka sosai sai sunan garin ya koma 'Kinkinau'. Wannan gari ya shahara qwarai da gaske a zamaninsa. Ya bunqasa da manyan Malamai Hausawa da Fulani waxanda su kan zo daga nisan duniya. Galibinsu su kan zo daga Zariya. Akwai xakin shari'a da gidan Alqali inda manya-manyan masana shari'a ke zuwa daga Zariya. Sai Garin Kinkinau ya yi ta bunqasa, ya yi kusan fin duk maqwabtan garuruwa.

Wannan gari mai ganuwa ya bunqasa sosai. An yi Sarakuna shidda kafin zuwan Turawa; (1) Kinkinau 1770-1810, da (2) Bajavvo (1810-1845), da (3) Allah Na nan (1845-1849), da (4) Dabo (1849-1869), da (5) Makama Etto (1869-1884), da (6) Abdullahi (1884-1909), a lokacinsa ne Turawa suka shigo wannan yanki na qasar Zazzau. Daga nan sai Sarki na bakwai (7) Muhammadu Abdullahi 1909-1934 da (8) Ibrahim Gani 1934. Daga nan sai wannan Sarkin ya koma garin Kawo sabuwa inda ya rasu a shekarar 1958. Sai Alhassan Abdullahi ya zama Sarkin Kawo (1958-1974) inda aka naxa shi Hakimi. Xansa Yahaya Ibrahim ya zama Sarkin Kawo.[1]

Wannan Gari ya bunqasa sosai. Babbar kotun shari'a da Alqalai masu ximbin sani da adalci sun havaka wannan gari. Jama'a daga nisan duniya na zuwa wannan gari don shari'a, da kasuwanci ko karatu. Hausawa da Fulani da Barebari sun havaka garin.

Lokacin da Turawa suka vullo har suka kafa garin Kaduna, Kinkinau babban gari ne. Mazaunan farkon garin Kaduna a wannan gari suke zuwa idan shari'a ta auku tsakanin Dungurawa, a kotun Alqalin wannan zamani suke kawo qara. Saboda haka sai wannan gari ya havaka sosai, ya koma ana kiransa Kangiwa.

Zuwan Fulani sabon garinsu, wato Kinkinau sai ya zama rahama ga Gbagyin wannan wuri, ballantana Gbagyin Kakuri kurmin Gwari. Kafin zuwan Fulani, Gbagyi na cikin tsoron farmakin Hausawan Afaka kamar yadda muka yi bayani a baya.

Zuwan Fulani ke da wuya sai suka qulla zumunci tsakaninsu da Gbagyi domin maqwabta ne. Kogin Kaduna ne ya raba su. Duk wani abin da zai cuci dabbobin fulanin Kinkinau sai Gbagyi su yi hanzari su sanar da Fulanin. Wani lokaci ma Gbagyi na taya Fulani aikace-aikacen gona ko aikin gini.

---

[1] Alhaji Kabiru Zubairu, *Kundin Tarihin Garin Barnawa*.

Saboda wannan zumunci da suka qulla tsakaninsu ne ma ya sa duk lokacin da Tuwa yaci Gbagyin Kakuri sai nan da nan Fulani su aika da shanu da hatsi garin Afaka domin fanso 'ya'yan maqwabtansu da aka kama. Su kuma Gbagyin sai a hankali su biya su. Sai wannan zumunci ya yi qarfi sosai tsakanin Fulani da Gbagyi. Sai aminci da zumunci suka kafu tsakaninsu. Fulani sun haxa kyakkyawar dangantaka tsakaninsu da Gbagyin Kakuri da Kudandan da na Kurmin Mashi.

Wannan dangantaka ta amfani Gbagyin matuqar gaske don sun sami sakewa da walawa da samun qarin tattalin arziqi ta wajen fannin kasuwanci da aikin gona. Wajen fannin siyasa, nan ma sun amfana, saboda da yawa daga cikinsu sun baro garuruwansu da ke Kurmi sun fito fili sun kuma kafa gidajensu a sarari ba tare da tsoron farmakin mahara ba. Idan ma an kai masu hari a akasarin lokaci, Fulani na taimaka masu. Amma duk da kariyar da Gbagyi suka samu dangantakarsu da Hausawa ba ta gyaru ba. Haka dai suke zaman doya da manja har vullowar Turawa.

Su Fulani, mutane ne ma'abota kiwo, domin duk inda suka ga ciyawa mai kyau sai su yi 'yan bukkoki a wajen. Saboda wannan hali su kan bar garuruwansu su tafi cikin jeji su yi bukkoki. Gbagyi kuma ma'abota yin gonaki nesa da garuruwansu ne. Su kan tafi wurare nesa da garuruwansu don aikin gona, sai su yi 'yan gidajen gona a gonakin nasu. Sai wannan halayya tasu ta yi kama da ta Fulani waxanda suke fitowa daga garuruwansu su tafi su kafa mashekari. Wannan hali nasu shi ya sa kake ganin su sun watsu a jeji, duk inda Fulani suka kafa mashekari sai Gbagyi su zo dab da su su kafa gona da 'yan gidajen gona saboda neman taki da kuma shaquwar da suka yi.

Dajin da ke Gabas da garin Kinkinau ko kuma dajin Doka, mallakar Fulani ne domin kyautar da aka yi masu don su yi amfani da shi wajen kiwon shanu. Shi wannan daji ba shi da daxin kiwo ballantana zama. Allah Ya yi wannan jeji da manya-manyan itatuwan doka kuma cike da namun jeji iri-iri.

Amma duk da haka, Fulanin sun yi amfani da gavar kogin Kaduna wajen kiwo. Saboda wannan kogi ya kusa ya yi wa wannan jeji qawanya, kuma gavar kogin akwai ciyayi koraye shar, abin da Fulani ke so.

Ko'ina aka yi gari, garin zai samu suna don 'yan-Adam suna da wannan hali na bai wa duk inda suka haxu suka kafa alqarya suna. Wannan ya taimaka wajen gane juna da sanin muhallin jama'a. Idan ka san sunan mutum, ba abin da za ka tambaya sai garinsa, daga nan sai gidansa. Matuqar an fahimci wannan halayya ta mutum, za a gane cewa abu ne mawuyaci mutane su haxu su kafa alqarya ba tare da bai wa alqaryar suna ba. Don haka duk inda kufai yake, to, yana nan tare da sunansa, wato dai sai an ce kufan gari kaza ke nan. Iyaye da kakanni za ka ji suna ba da labarin garin, duk lokacin da za a wuce kufan garin, wani lokaci kuma ana yin kwatance da kufan garin. Ta haka, abu ne mawuyaci sunan gari ya vace

matuqar an kafa shi komai qanqantarsa. Dalilin da ya sa har gari ya fashe, ya zama kufai za ka ji tsofaffi na ba da labari, ta haka sai ka ga kufai shekaru masu yawa ba a manta da garin ba.

Saboda waje ne mai wuyan zama, sai dajin Doka ya gagari kafa gari, wannan dajin fulani ba su more shi ba, saboda suna ji suna gani suka kewaye shi, suka tafi suka kafa sabon gari. A cikin shekarar 1870 sai wasu rukunin Fulani suka tashi, suka kwashi kayayyakinsu suka kuma sanya shanunsu a gaba suka yi Gabas. Sai da waxannan Fulani suka keta dajin Doka, suka shilla, sai da suka tarar da bakin kogi. A wajen da suka sami itacen kawo sai suka kafa bukkokinsu. A wannan gavar kogin Kaduna sai suka kafa garin Kawo, wanda ya samo suna daga itacen kawo.

Tashin Fulani daga garin Kinkinau bai fasa garin ba sai jama'a suka ci gaba da harkarsu kamar da, irin wannan halayya ta Fulani sananna ce, ana zaune da su shekara da shekaru sai kwatsam ka wayi gari ka ga sun tashi zuwa wani wuri. Hausawa sai qara zuwa suke ta yi daga Zariya, har lokacin da aka kafa garin Kaduna jama'a sun zo sun qara bunqasa wannan gari.

Tashin waxannan Fulani ya baqanta wa Gbagyi rai, saboda rashin maqwabta da suka yi. Saboda zumunta a qafa take, Gbagyi kan niqi gari su tafi garin Kawo inda Fulani suka koma don sada zumunci, an cewai wasu ma sun kafa 'yan garuruwa kusa da su saboda shaquwa. Don nuna so da qauna ga Fulani, sai kirari Gbagyi ke yi wa shugabannin Kinkinau waxanda suka koma garin Kawo da zama. Su kan ce da su "Cicininau wargin Beguwa, Allah Ya ba ka rana cikin daji. " A nan, Gbagyi na yi wa shugabannin Fulani kirari da cewa ba su da dama wajen daga, amma Allah Ya ba su sa'ar yaqi.[1]

Garin Kawo

Kirarin wannan gari, "Kawo namijin gari komai ka gani a kawo, kawo shi aka yi!" Fulanin Kawo daga garin Kangiwa suka zo shekaru masu dama kafin vullowar Turawa. Zuwan waxannan Fulani bakin kogin Kaduna ta fuskar Gabas, sai suka tarar da wani qaton itacen kawo tare da wata itaciyar kanya. A wannan waje sai suka kafa bukkokinsu a wannan ruga wadda ta shiga havaka cikin hanzari.

Zamansu a wannan wuri sai suka sa wa wajen 'Kawo' saboda wannan itace da ke wannan wuri. Suna nan zaune a bakin wannan kogi amma zumuncinsu da Gbagyin Kakuri da Kudandan maqwabtansu a da, na nan sosai. Wannan unguwar Kawo sai ta fara bunqasa.[2]

---

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Alhaji Ibrahim, ran 20 ga Disamba 1984.

[2] *Ibid*.

Kawo gari ne mai tsohuwar masarauta, an ce ita ke mulkin gargajiya a wannan yanki, shekaru masu yawa da suka wuce. Ana jin ma kusan lokaci guda Fulani suka watsu zuwa Barnawa da Kinkinau da Kawo, inda rugagensu a waxannan wurare suka bunqasa har suka zama garuruwa. Qasidar Sambo ta ce:

"Alal haqiqa asalin dai garin Kaduna tana qarqashin mulkin gargajiyan Sarkin Kawo ne. Shi kuwa qauyen Kawo asalin mazauna cikinsa su ne Fulani waxanda su (Fulani) suka kafa qauyen tun shekarar 1700, wato kafin hijirar Shehu bin Fodio a shekarar 1802. Qauyen Kawo an kafa shi da daxewa. A qauyen Kawo ne jama'ar lokacin ke taruwa musamman ma 'yan kasuwa masu yin safara, wato mahaxar 'yan safara, kafin su tafi safaran kasuwanci zuwa Gwanja (a Ghana), waxansu daga cikinsu a kan jakuna, wasu raquma ko shanu, wasu kuma a qafa. "[1]

Marubuta masu dama sun faxi cewa, Fulani sun shigo lardin Zazzau ne shekaru da dama kafin varkewar jihadin Shehu Usman Mujaddadi. Da yawa sun zauna a Zariya, wasu kuma suka kwararo zuwa yankin kogin Kaduna inda suka kafa rugagensu a Kinkinau, da Barnawa, da Kawo da sauran wurare da ke Arewaci da kudancin Kogin Kaduna. Daga Fulani, sai Barebari suka kwararo zuwa cikin wannan lardi.

Wanda ya fara sarauta a wannan sabon waje shi ne, Magaji Hukau daga shi sai Garba Abbas.[2] Suna nan zaune har aka kafa garin Kaduna. A wannan lokaci har an soma gidajen 'yan bita da barikin sojoji a bakin hanyar jirgi zuwa Rigacikun.

A hankali sai jama'ar unguwar Kawo suka fara fitowa daga Kawo ta bakin kogi, suna kafa gidaje kusa da 'yan bita. Cikin xan qaramin lokaci, sai gidaje suka cika bakin hanya. Saboda sun matsi Barikin soja wato Barikin Dalet, sai aka tashi jama'ar wurin baki xaya aka dawo da su inda Kawo take yanzu. Lokacin da ake tasowa daga tsohuwar Kawo zuwa bakin hanya, wanda yake sarautar Kawo a wannan lokaci, shi ne Sarkin Kawo Abdullahi. Shi Sarki Abdullahi ya samu shekaru goma sha-takwas yana sarautar Kawo kafin ya yi ritaya xansa ya hau sarautar. Zuriyarsa ke sarautar Kawo da Unguwar Shanu da sauran garuruwa.

Sarkin Kawo Abdullahi yana da 'ya'ya huxu: Muhammadu, da Ibrahim, da Alhassan da Husaina (Hasana yar tagwaitakarta bata daxe ba ta rasu). A lokacin da yake sarautar Tsohuwar Kawo garin ya bunqasa sosai. To, ga lokaci ya zo jama'a na tashi zuwa Sabuwar Kawo. Saboda ya tsufa sai ya yi murabus, sai xansa Muhammadu Abdullahi ya karvi sarautar a (1909-1934). Shi ne Sarkin sabuwar Kawo na farko.

Sarkin kawo Muhammadu ya samu 'yan shekaru yana sarauta, sai Magajin Gari Sambo ya kawo wasu sauye-sauye a harkar sarautar Kaduna da kewaye. A

---

[1] Abdulqadir Yero Sambo, *Qasidar Tarihin Kaduna* shafi na 4

[2] Alhaji Kabiru Zubairu, *Kundin tarihin Barnawa*

wannan shiri sai ya xauki wannan Sarki daga Kawo ya kai shi Tudun-Wada Kaduna a matsayin Sarki. A wannan lokaci sai ya naxa qanin wannan Sarki wato Ibrahim Abdullahi matsayin Sarkin Kawo.

Sarkin Kawo Ibrahim ya samu kusan shekaru arba'in yana sarauta, qaninsa kuma Alhassan Abdullahi na riqe da muqamin Ciroman Kawo, sai aka naxa shi sarautar Unguwar Shanu. Yana kan gadon sarautar ne sai likkafarsa ta yi gaba aka naxa shi Hakimin Kawo. A wannan sabon shiri sai wansa Ibrahim Abdullahi da ke sarautar Kawo aka koma da shi sarautar Unguwar Shanu.

Da Alhassan Abdullahi ya zama Hakimin Kawo sai ya naxa xansa Yahya Alhassan Sarautar Kawo, wanda aka fi sani da Yahya Ibrahim saboda a hannun wan mahaifinsa Ibrahim Abdullahi ya girma. Hakimin Kawo Alhassan Abdullahi ya rasu a shekarar 2002. Sai xansa Jibrin Muhammad Sani ya gaji sarautarsa.

Unguwar Shanu, da Unguwar Rimi, da Unguwar, da Kabala Kwastin, da Kabalar Doki, da Badarawa, da Malali, da Rafin Guza, da Unguwar Gwari, da Hayin Banki da Kurmin Mashi duk suna qarqashin sarautar Kawo ne. A shigowar Fulani qasar Zazzau sun watsu a wurare masu yawa a cikin wannan lardi. Babu wani takamanman lokaci da za ace sun shigo, amma masana tarihi su kan ce a shekaru masu yawa kafin jihadin Shehu ne. A wannan lokaci ne wani Bafilatani ya kafa wata ruga da ta yi suna a gavar kogin Kaduna, wato Rugar Muhammadu Dindima. Zuwan Barebari wannan ruga ne, ya bunqasa kafuwar Barnawa.

Vullowar Barebari

An kafa garin Barnawa cikin qarni na goma sha-shida 1650. Wanda wani Bafilatani mai suna Muhammadu Dindima ya kafa a zamanin Sarkin Zazzau Ibrahim Basuka a shekarar (1641-1654) da ke cikin Sarakunan Have. An kafa wannan gari shekara xari da hamsin da huxu (154) kafin bayyanar Shehu Usmanu Xan Fodiyo. A yanzun wannan gari yana da shekara xari uku da hamsin da uku (353).

Da farko ana kiran wannan waje "Rugar Dindima. "A hankali sai wajen ya havaka sosai har ya zama gari, amma babu wani suna da garin ya yi kafin zuwan Barebari, amma akwai shi da tsarin mulki kafaffe. Wannan Rugar Dindima ta yi suna sosai, har ta kai matsayin gari. A wannan garin an naxa Sarakuna goma sha-shidda daga shekara 1650 zuwa 2003. Ga tsarin Sarakunan kamar haka: (1) Muhammadu Dindima, 1650-1707, (2) Jimau Dindima 1707-1742, na uku (3) Idrisu Dindima 1742-1793, na hudu (4) Amana Dindima 1793-1842, a zamaninsa ne Shehu Usman ya bayyana, na biyar (5) Magaji Kukau 1842-1886, na shida (6) Magaji 1886-1922, a zamanin sane Turawa suka zo Kaduna, (7) Magaji Muqaddas 1922-1926, (8) Magaji Kabi'u 1926-1935, (9) Magaji Guruza 1935-1940, (10) Muhammadu Lamu 1940-1947, (11) Sarkin Fulani Ibrahim Yamusa

1947-1948. Duk waxannan Sarakuna sun yi mulkinsu a tsohon gari da ke bakin Kogin Kaduna.

Daga nan sai Barnawa ta dawo inda take yanzu wato Sabuwar Barnawa saboda ambaliyar ruwa da yawan mace-macen jama'a da ciwon makanta, da mutuwar Sarakuna duk sun haxu sun tarwatsa wannan tsohon gari. A sabuwar Barnawa Sarakuna sun ci gaba da mulki (12) Waziri Musa 1948-1955, (13) Muhammadu Lawal 1955-1992, (14) Magaji Idrisu 1992-1999, (15) Magaji Kabiru Zubairu 1999-2002, Magaji Habibu Zubairu 2002 - yanzun.[1] Fulani suka kafa harsashin wannan gari bayan shekaru tamanin da huxu sai Barebare suka shigo wannan waje. Amma duk inda Fulani suke zaune ba ka rasa Gbagyi saboda zumunci da taimakekeniya da juna da suke yi.

Bunqasar Zazzau da mulkinta sun zo qarshe bayan da Barebari suka qwaci mulkin Zariya ba tare da yaqi ba a shekarar 1734! Zariya wadda ta mallake qasashen Hausa sai ga ta kwatsam qarqashin mulkin Barno. Daga wannan lokaci sai ta koma kai haraji ga Barno a kowace shekara, wato dai sai da ta xanxana irin Mulkin Mallakar da ta saba nuna wa sauran qasashen Hausa.

Da mulkin Zazzau ya koma hannun Barno, sai Shehun Barno ya aiko da wakilansa guda biyu, xaya zuwa gidan Sarautar Zazzau, xaya kuma zuwa babbar kotun shari'ar Zazzau. Duk wani abin da zai wakana a waxannan wurare sai da iznin Shehu. Kowane Sarki idan za a naxa shi, to, wakilin Shehun wanda ake kira Magajin Malam shi ke naxa su. Aikin Magajin Malam ne naxa Sarakunan Zazzau, wato dai shi ne wakilin Shehun Barno mai kula da naxin sarauta.

Haka kuma shi ne mai kula da sha'anin shari'a a babbar kotun Zazzau mai suna Kacalla, aikinsa ne na tabbatar da duk ayyukan shari'a a kotun Zazzau, Shehun Barno na samun isasshen rahoto. Magajin Malam da Kacalla su ke tabbatar da mulkin Barno a Birnin Zazzau. Haka dai Zariya ta ga wannan Mulkin Mallaka har vullowar Jihadin Fulani. A wannan zamani, an cewai rukunin Barebari da yawa sun shigo lardin Zazzau, da yawa daga cikinsu sun zauna a Zariya.

Garin Barnawa

A lokacin da Barno ke mulkin Zariya, wato bayan shekarar 1734, wani rukunin Barebari qarqashin wani babban Malami, kuma waliyin-Allah sun zarto kudancin Zariya inda suka zauna a rugar Fulanin da ke Gabas da Kakuri a inda suka tare a Rugar Dindima. Wannan rugar Fulani ta samu shekaru kusan 84 da kafuwa kafin zuwan Barebari, kamar yadda aka yi bayani a baya. Wata qila, a zamanin Sarkin Zazzau Xan Ashakuka (1734-1737), Barebari suka shigo wannan waje.

---

[1] Alhaji Kabiru Zubairu, *Kundin Tarihin Garin Barnawa*.

Shugaban wannan rukunin Barebari, shi ne Malam Kilba. Malam Kilba, bab-ban malami ne mai ximbin ilimin kuma waliyin-Allah. Saukar Barebari a wannan ruga ta Fulani ta bunqasa garin sosai. Cikin hanzari gari ya tashi havaka, aka kuma sa wa garin suna "Barnawa " saboda bunqasar da ya samu domin zuwan Barebari. Wannan gari ya samu sunansa ne daga Barno (wato dai Barno-Barnawa, kamar yadda ake cewa Kano-Kanawa). Kafa wata mashahuriyar makaranta da wannan Bawan Allah Ya yi, ta xaukaka wannan waje.

Malam Kilba ya buxe makaranta babba a wannan gari wadda ta yi tashe a lardin Zazzau a wannan zamani. Hausawa da Fulani da Barebari sai zuwa suke ta yi neman karatu da tabarraki wurin wannan babban Malami, jim kaxan sunan garin Barnawa ya danne sauran garuruwan da ke maqwabtaka da shi. Malam Kilba ya samu shekaru saba'in a garin Barnawa kafin Mujaddadi ya bayyana. Saboda haka a wannan lokaci malamin ya tsufa sosai.

A lokacin da Shehu Mujaddadi Usman Bin Fodiyo (Allah Ya qara yadda da shi) ya bayyana, sai ya aiko wa Malam Kilba yana bixar sa wajen batun Jihadi. Amma a wannan lokaci babban Malamin ya tsufa, sai ya aika da almajiransa guda biyu a madadin kansa. Malam Kilba ya aika wa da Shehu Xan Fodiyo da manyan almajiransa waxanda suke karatu a wajensa a garin Barnawa. Sunan waxannan almajiran su ne, Musa Bamalli da Yamusa (wanda yake Fulato-Barno ne).

Saboda haka ne sai Musa Bamalli da Yamusa suka tafi wajen amsa kiran Shehu Mujaddadi domin umarnin malaminsu. Waxannan manyan almajiran Malam Kilba Allah Ya ba su haziqanci da fasaha da kwarjini ga kuma ximbin karatu. Saboda waxannan baiwoyi da Allah Ya ba su, don haka ne ma Malam Kilba ya tura su zuwa wajen Shehu domin su wakilce shi.

Malam Musa Bamalli da Malam Yamusa sun bar garin Barnawa zuwa wajen Shehu Usman Mujaddadi a cikin farkon shekarar 1804. Sun karvi tutar Jihadi daga wajen Shehu a wannan shekara, an kuma buqace su da zuwa Zariya. Malam Musa Bamalli a matsayin liman, wato kamar matsayin Sarki ke nan, Malam Yamusa kuma a matsayin Madaki. Sun nufo Zariya domin yin Jihadi wato xaukaka sunan Allah. Almajiran Malam Kilba da suka karvi tutar Jihadin wurin Shehu Mujaddadi tare da askarawan Jihadi xari uku da talatin da uku (333), sun auka wa Zariya da yaqin xaukaka sunan Allah, ranar Asabar goma ga watan Zul-Hajji 1804 A.D. A safiyar wannan rana ce askarawan Shehu suka gwabza da Zage-zagi.

Wanda ke sarautar Zazzau a wannan lokaci, shi ne Sarkin Zazzau Muhammadu Makau. A wannan ranar Sarki Makau da jama'arsa suna bayan gari wajen Sallar Idi. Bayan da aka idar da salla, sai Sarkin ya samu labarin cewa ai Fulani sun mamaye Zariya. Ko da yake Sarkin Zazzau Muhammadu Makau na tare da jama'arsa, amma an immasu saboda dakarun yaqinsa ba su samu damar shiga Zariya ba domin su yi shirin yaqi ko kuma su kwashi kayan yaqi. Nan

jama'ar Sarki Makau suka yi ta artabu da askarawan Jihadi, daga qarshe dai sai Sarkin ya gudu, wato dai an ci Zariya ke nan. Sarki Muhammadu Makau ya sha fama da Fulani, amma daga qarshe sun samu immasa a cikin shekarar 1825 A.D.

Malam Musa Bamalli sai ya zama Sarkin Zazzau na farko a mulkin Fulani, shi ne kuma ya kafa gidan Mallawa (Mallawa Dynasty), a sarautar Zazzau. Ya yi sarautar Zazzau cikin shekarar 1804 zuwa 1821. Bayan rasuwar Sarkin Zazzau Malam Musa Bamalli, sai Madakinsa Malam Yamusa ya hau gadon sarautar Zazzau. Shi ne ya kafa gidan Barebari a sarautar Zazzau (Barno Dynasty), shi ma ya yi sarautar Zazzau cikin shekarar 1821 zuwa 1834.

Allahu Akbar! Barnawa babban gari ne a wannan lokaci, almajiran Malam Kilba waxanda suka yi karatu a Barnawa duk sun yi sarautar Zariya wadda ta mallaki makekiyar qasa da qabilu iri-iri. Allah Ya jikan wannan babban Malaminsu da askarawan Jihadi, Allah kuma Ya qara wa Shehu Usman Xan Fodiyo karama amin. An daxe jama'a na zuwa ziyarar kabarin Malam Kilba daga kusa da nesa a qasar Hausa. An ce ma kabarin nasa na haske in dare ya yi. Tsohon garin Barnawa ya daxe yana samun rukunin jama'a masu zuwa ziyara. Amma yanzu a kufen wannan gari babu inda za a gane wannan kabari saboda ya vace.

Idan muka dawo yaqin Jihadi a Zariya kuwa sai a ga irin wannan sabon salon hari na far wa jama'a bayan sallar idi, ya sa sauran garuruwan sun yi nadama. Ganin yadda aka yi wa Sarki Muhammadu Makau ya karya zukatan waxansu qasashe. Saboda gudun irin wannan hari, sai wasu qasashe suka riqa yin sallar idi a cikin garinsu ba a fita bayan gari yin Sallar Idi ko da an fita, to, sai a tafi da shirin yaqi saboda tsoron harin ba-zata.

A lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim, garin Barnawa ya samu Sarki, wanda aka naxa kuwa, shi ne Malam Musa. Ya samu shekaru takwas da rabi yana sarauta kafin Allah Ya yi masa rasuwa. Ya rasu a lokacin Sarkin Zazzau Malam Jafaru Xan Isiyaku. A cikin shekarar 1948, Sarkin Zazzau Malam Jafaru ya naxa Alhaji Muhammadu Lawal Sarautar Barnawa. Wannan gari ya bunqasa sosai har ma akwai wata dangarankar garin da Fulani Sarakunan Zazzau. Sarki Lawal a wani zama na zantawa a kan tarihin Kaduna, ya yi qari da cewa:

"Tun a Dungurun kakanku Malam Isa ke ba Turawa mamaki. Saboda haka ne suka naxa shi Sarkin Alaro. Turawane suka naxa shi wannan muqami, tun kafin a tare Kaduna. Dungurawa suka tare a sabon waje saboda haka a idonmu aka yi komai a wannan gari. "[1]

Tarihi yauqi ne da shi, wajen ba da tarihin Kaduna wani lokaci sai an haxa da na Dungurun sannan ya tafi dai-dai. A wani lokaci kuma sai an haxa shi da tarihin

[1] Hira da Sarkin Barnawa Alhaji Muhammadu Lawal a gidansa a ran 24 ga Janairu, 1985. A lokacin yana da shekara 82 da haihuwa.

Zazzau ko kuma tarihin Arewa. Domin kuwa wannan gari ya haxa tarihin waxannan wurare baki xaya. Haka kuma wannan Sarki ya qaryata iqirarin da ake cewa Barnawa gari ne na Gbagyi. Ya ce tun fil azal wannan garin Fulani da Barebare ne, ba su kuma tashi kowa ba wajen kafa shi. Wani abin lura kuma abin assasawa a nan shi ne babu wani garin wata qabila da aka tarar a wannan dajin Allah. Wani tsohon soja mai shekaru xari da goma sha-huxu mai suna Musa Hamvago da ke zaune a Tudun-Nufawa wanda ya yi yaqin duniya na xaya cewa ya yi: "Mun ta yin karakaina bisa jirgin kwakwalgi (wato jirgin qasa mai aiki da itace) a tsakanin garin Baro da Birnin Kano, a lokacin da hanyar jirgi ta samu. Mu kuma ma'abota shiga daji ne, amma ba mu ga wani garin qabilar Gbagyi a dajin Doka ba. Amma idan ka shiga daji sosai gaba da Badikko, akwai Kurmin Mashi. Amma ana samun xaixaikun mutane suna fitowa daga garuruwansu su zauna da su da Fulani a daji kamar maharba. "[1]

Barnawa Cibiyar Sarakunan Zazzau

Ana jin musulunci ya shigo lardin Zazzau a qarshen qarni na goma sha-biyar. A zamanin Sarkin Have, Malam Abu a shekarar (1505 zuwa1530) ake jin cewa musulunci ya fara samun karvuwa ga Sarakunan Have, ya kuma fara kafuwa a lokacin Bakwa Turunku a shekarar (1536 zuwa 1539). An ce shi Bakwa Turunku Musulmi ne mai suna Isiyaku. Ya yi kuma zamani ne da Muhammadu Korau na Katsina da Muhammadu Rumfa na Kano. Dukkansu tarihi ya nuna cewa mashahuran Sarakuna ne a qasar Hausa waxanda suka yi suna wajen mulki da adalci kuma sun taimaka gaya wajen kafa musulunci a lokacinsu.

A lokacin Sarkin Zazzau Jatau, musulunci ya kafu sosai, wannan ya sa ma wannan Sarki ya gina Masallacin Juma'a a Unguwar Juma. Shi Sarki Jatau yana mai goyon bayan Shehu Xanfodiyo tun lokacin da ya fara wa'azinsa a garin Gobir. Suna kuma mu'amula da juna tun kafin varkewar yaqin jihadi. Ana jin cewa Mujaddadi ya xalibci mashahuriyar makaranta da ke Limanci Kona.

Haka kuma wannan Sarki mai kishin Islama ya kawo wa Zazzau bunqasar arziqi da siyasa tare da addini. Ya rasu a qarshen shekarar 1802. Amma abin takaici xansa Makau wanda ya gaje shi, sai ya kafircewa shirin da ubansa ya xora shi a kai. Albasa ba tai halin ruwa ba, sai Makau ya zama kamar Yunfa xan Sarkin Gobir Bawa Jan Gwarzo. Ya zama ba abin da yake zumuxin yi sai ya rusa musulunci a qasar sarautarsa. Saboda haka ya zama mai bin umarnin Yunfa sau da qafa.

Sarkin Gobir Yunfa, da ya kafa dokar ta vaci a qasar Hausa, sai ya nuna wa Sarakunan Have mabiyansa yadda za su kashe wannan wuta ta Islama da ta taso daga qasarsa. Su kashe Malamai. Saboda haka kafin ka ce me! Har ya kai yaqi ga

[1] Hira da Alhaji Musa Hamago a ranar 17 ga watan Satumba 1984.

wata alqarya babba daga cikin alqaryun Musulmi, a lokacin da mutanensa suka kashe jama'a da yawa daga cikin Musulmi, musamman malamai da mahardatan Alqur'ani. An yi wannan varna da rana, cikin watan Ramalan mutane suna azumi.[1]

Don haka Sarkin Zazzau Makau ya zama mai zaqewa wajen bin umarnin da Sarkin Gobir Yunfa ya aika wa duk Sarakunan Have a qasar Hausa, inda ya ce da su: "Na bar wata qaramar wuta a qasata, na kuma kasa kasheta, ga ta ta ruru sosai za ta kuma halaka ni. Na gargaxe ku, ku lura kada ku faxa mata kuma ta halaka ku. "[2]

Wannan mummunan umarni ga dukkan miyagun Sarakunan Have qaimi ne wajen yaqi da musulunci. Sun kuma fito haiqan wajen kashe wannan wuta ta hasken musulunci da ta fito daga Gobir. Amma Sarkin Zazzau Makau shi ya fi zaqewa wajen hure wannan wuta ta Islama wadda haskenta ke qaruwa a idonsa a kuma qasarsa. To, tun da sunansa "Makau " ba abin yi sai ya "make " Musulmi don cimma wannan mummunan buri.

Sarkin Zazzau Makau na hawa karagar mulki a shekarar 1802 sai ya yi yunquri mai qarfi wajen rusa Addinin musulunci a qasar Zazzau. Ya yi watsi da yarjejeniyar tu'amuli da juna da ubansa Jatau ya yi da Shehu Usman Xanfodiyo don ya azabtu da masifar qin musulunci da musulmai. Don haka ne malamai da yawa suka yi shahada a hannunsa. Masallacin Juma'ar da mahaifinsa ya gina a Unguwar Juma bai vata lokaci ba wajen sa wa a rushe shi, ya kuma fito firi-falo ya hana wa'azi da karantar da Addinin musulunci. Ya xauki salo da halayyar Sarkin Gobir Yunfa ya bi kuma umarnin da ya bayar ga Sarakunan Have da duk inda suke su kashe fitilar musulunci. Makau shi ne kan gaba wajen bin wannan doka don ya zaqe wajen kare Maguzanci a qasarsa.

A cikin mashahuran malaman da suka zo Zazzau a lokuta daban-daban, tun kafin varkewar jigadi akwai Malam Musa Bamalli, da Malam Yamusa Babarbare da Malam Abdulkarim Bakatsine wanda ya zauna a gidan limamin Kona Malam Ahmadu Mai Jan Riga. Koda na tambayi Malam Tanimu Zariya wanda gidansu fitacce ne a Kusfa, ko me ya sa ake cewa wannan mashahurin limami, mai Jar Riga? Sai ya ce da ni, "malami ne wanda ya yi nisa wajen Ijtihadin roqon Allah. A zamaninsa quda ko qwaro ba ya hawansa ya tashi, don kuwa da ya tava jar rigarsa, to, kwanansa ya qare ke nan. A inda ya zauna, haka za ka ga qudaje matattu birjik. "[3] Ajali ya kaisu sauka a kan Mai Jar Riga, kai ka ce an fesa masu maganin qwari ne. Amma babu magani a wannan rigar. Shiri ne irin na 'maza

---

1 *Imfaqul Maisuri* na Muhammadu Bello Fassarar Sidi Sayuxi da Jean Boyd (1974) shafi na 16.

2 Arnett E.J. *Gazetteer of Sokoto Province in Nigeria; Northern Nigeria, London*: Waterlow and Sons Limited, 1920, shafi na 20.

3 Hira da Malam Tanimu Zariya, ran 4 ga Satumba 1984

tuwon qaya miyar allura' da ya dace da wannan lokaci. Qwari suna tava malam, suna kwana qiyama, to, wa zai kawo masa wargi? Bai kamata mu yi amfani da fahimtar mu da wayewar mu a yanzu mu hukumta waxannan malamai ba. Saboda gwagwarmayar zamaninsa ya bambanta da tamu. Don kuwa addini da imaninsu da dabarun yaqinsu sun yi tasiri mai kyau, soboda haka ne ma musulunci ya kawo gare mu.

Malam Tanimu Zariya aminin Limamin Kona Malam Aminu ne, ya kuma so ya kai ni makarantar da Shehu xan Fodiyo ya halarta a gidan Limamin Kona cikin birnin Zazzau, amma Allah bai nufa ya sami damar yin haka ba. Amma Allah Ya bani izinin ziyarar wannan mashahuriyar makaranta bayan shekara ashirin da rasuwar Malam Tanimu Zariya.

Limaman Kona sun shahara wajen ilimi da taqawa da karama. A wajen Liman Kona Hami (Hamidu) Shehu xan Fodiyo ya yi karatu, inda ya samu 'yan shekaru yana zuwa wajen wannan Malami yana karatu a Birnin Zariya. A wannan lokaci Ahmadu Mai Jar Riga xan Limamin Kona Hami yana qarami. Gidan waxannan limamai ya taimaka gaya wajen yaxa Addinin musulunci ba a Zariya ba, har ma a Nahiyar Afirka baki xaya.

Irin wannan shiri na liman Ahmadu Mai Jar Riga ya yi tasiri sosai. Musamman in aka yi la'akari da qoqarin da Sarkin Zazzau Makau ya yi na neman ya tuge musulunci da qarfin tsiya don kafirci ya kafu sosai. Wannan Sarki ya 'Make' maluman Addinin musulunci da dama ya kuma rushe masallatai. Amma ya yi karo da Mai Jar Riga, tare da sauran malaman sunna waxanda suka yi jihadin kare Addininsu.

Allahu Akbar! Bayan Makau ya rushe Masallacin Juma'ar Unguwar Juma, sai ya kashe limamin masallacin Malam Muhammadu Lawal. Shi wannan Limami ya yi shahada ne saboda ya fito fili yana addu'a ga Allah Ya taimaki musulunci da musulmai, ya kuma qasqantar da kafirci da kafirai. Allah kuma Ya kawo wa Zazzau limami wato shugaba wanda zai riqa zuwa masallaci.[1] Wannan addu'a ta hassala Makau ainun. To, tun da Makau shugaba ne mai mugun nufi ga musulunci me zai sa shi shiga masallaci. Sai Makau ya make wannan malami mai addu'a. Allah Mai girma Ya amsa roqon wannan shahidi, ashe Malam Musa Bamalli da Malam Yamusa na tafe da rundunar 'yan jihadi.

Amma kafin varkewar yaqin jihadi a Zazzau, hankalin Musulmi ya tashi qwarai saboda ganin yadda Makau ya taso haiqan wajen neman ya hure wutar Islama a qasar Zazzau. Da Sarki Makau ya lura cewa kashe malamai shi zai sa ya cimma mugun burinsa, sai ya nufi Limamin Kona inda nan ne tushen musulunci yake a qasar Zazzau baki xaya. Amma sai Liman Ahmadu Mai Jar Riga ya gagara tavuwa. Malamai kuma sai suka shiga roqon Allah da Ya yi masu maganin

[1] Usman Xalhatu, Malam Ja'afaru Xan Isiyaku: *The Great Emir of Zazzau*, shafi na 32.

wannan bala'i. To gashi Allah kuma Ya karvi roqon bayinSa salihai, Ya turo masu 'yan jihadi qarqashin Malam Musa Bamalli da Malam Yamusa Babarbare. Suka kori Makau suka jaddada Islama a lardin Zazzau. Allah Ya kawo limamai shugabanni masu shiga masallaci, Zariya kuma ta zamo mavuvvugin ilimin Addinin musulunci fitacce, ba a Nijeriya kawai ba, a duniya ma baki xaya.

Kamar yadda M.G. Smith ya nuna a littafinsa mai suna *Government in Zazzau* (1800-1950) tun kafin jihadin Shehu Usmanu na shekarar 1804, akwai Fulani a cikin garin Zariya. Akasarinsu malamai ne masu wa'azi da karantarwa. An ce a cikin birnin Zariya, akwai Liman Xan Madami wanda yake tu'amuli da Malam Musa Bamalli har wajen shekaru bakwai kafin yaci Zazzau da yaqin jihadin Shehu Usmanu. A wannan lokaci akwai Fulani a garin Barnawa Smith, masanin tarihin ya yi nuni da cewa:

"Kusan mil 50 a kudancin birnin Zariya akwai tushen Fulani guda biyu: Fulanin Barnawa, qarqashin shugabancin Malam Yamusa da qanensa Babaiyo, da Fulanin Sulluvawa, qarqashin Malam Kilba da xansa Abdulsalami. Haka kuma a tsakanin kogin Kaduna da Zariya akwai wani jinsin Fulani Sulluvawa, qarqashin Ja'e. Akwai wasu Sulluvawan Fulani a Kwassallo da Ricifa da suke Arewa maso Gabashin birnin Zazzau suna zaune da iyalansu. Su waxannan Fulani sun shiga yankin Kano a lokacin da yaqin jihadi ya varke. Daga bisani kuma suka zama shugabannin waxannan garuruwan. "[1]

A dalilin haka Fulani Sulluvawa sun daxe a Zariya. Tun kafin Malam Musa Bamalli ya far wa Zariya da yaqin jihadi, Sulluvawan Igabi da na Barnawa sun daxe da qulla danqon zumunci tsakaninsu, wannan ya sa ma har Malam Yamusa ya auri yar Malam Kilba. Dukkansu Barebari ne.

Sulluvawan Zazzau sun kasu kashi biyu: Akwai vangaren Ja'e, a garin Ricifa da na Abdulsalam na Barnawa. Abdulsalami Bafilatani ne, Basulluve wanda ya riqe muqamin Makama a zamanin mulkin Sarkin Zazzau Malam Musa Bamalli, shi ne Sarkin Zazzau na bakwai. Ya yi shekaru huxu yana mulki daga shekarar (1853 zuwa 1857 A.D). Shi ne kuma ya kafa Gidan Sulluvawa, xaya daga cikin gidajen sarautar Zazzau. Wannan ya nuna akwai Fulani a sassa daban-daban a cikin lardin Zazzau tun kafin jihadin Shehu Usman Xanfodiyo.

Kamar yadda M.G. Smith ya yi nuni da cewa Malam Musa ya ziyarci birnin Zazzau a lokuta da dama a wasu shekaru kafin varkewar jihadi, har ma ya ce Malamin ya karantar da Alqur'ani a cikin Zariya, yana kuma kaiwa da komowa a

---

[1] M.G. Smith, *Government in Zazzau*, (1800-1950), Oxford University Press, London (1960) shafi na . 137-138.

tsakanin garuruwan Igabi da ke kudancin Zariya.[1] Saboda haka yana kuma sane da Malam Kilba da iyalansa da Malam Yamusa waxanda suke zaune a garin Barnawa. Wata qila a lokacin da yake karantarwa a Zariya yana kuma xalibci a garin Barnawa.

Har ila yau, kamar yadda wannan marubucin ya faxa, an ce Fulanin Barnawa da Sulluvawa da ke wannan yanki na Zazzau su na qarqashin shugabancin Malam Yamusa ne wanda har ma ya cewa Mujaddadi ai su ne Fulani 'yan asalin Zazzau, saboda haka ba sai an naxo masu shugabanni ba. An ce ya so a naxa shi mataimakin Shehu a lardin Zazzau, ko kuma a ba shi kudancin Zariya da mulki. Amma sai aka lallashe shi da ya zama mataimakin Malam Musa Bamalli wanda Shehu ya bai wa tutar jihadin xaukaka kalmar Allah a lardin Zazzau.

A wani qaulin kuma, an ce Shehu ne ya umurci Mallam Musa da ya haxa kansa da su Malam Yamusa da Abdulsalami Basulluve tare da Malam Abdulkarim, wani Bafilatani al'majirin Shehu daga Katsina. Mai yiwuwa Shehu ya bayar da waxannan umurnai ne bayan ko kuma kafin Malam Yamusa ya yi qorafin kada a kawo masu shugaba daga waje, mai yiwuwa ne ya ba da wannan hanzari ne kafin, ko kuma bayan varkewar jihadi. Duk waxannan qauloli sun nuna qarfin Fulani da haxin kansu wajen ci gaban Zariya da yaqi da kuma neman mulkinta. Bugu da qari, sun nuna qarfi da muhimmancin garin Barnawa a wannan zamani.

Har ila yau idan muka dawo garin Barnawa, za mu ga cewa, ai qasaitacce kuma fitaccen gari ne mai tsohon tarihi. Haka kuma cibiyar yaxa Addinin musulunci ce babba, wadda ta yi suna wajen fidda mashahuran malamai kuma Sarakunan Zazzau. M. G. Smith ya ce Malam Musa Bamalli na tare da Mujaddadi a lokacin da ya yaqi Sarkin Gobir Yunfa. Ya kuma ce an qwama da shi wajen yaqin Kano, tun kafin a ba shi tutar jihadi. Daga Kano ne aka ce ya dumfaro Zariya da askarawa da barade saba'in da huxu a kan dawakai. Yaci karo da maguzawan garin Kudan da ke tsakanin Zariya zuwa Kano, a inda ya sami taimakon Musulmi da ke qauyen Zabi, nan da nan ya bi takan Kudan ya cinna mata wuta.[2]

Mai yiwuwa daga Barnawa Malam Musa ke tafiye-tafiye da yaqe-yaqensa inda har ma ya nuna jaruntaka, ilimi da taqawa da sanin makamar mulki, wasu kyawawan halayen da suka sa Shehu Mujaddadi ya ba shi tuta. Ya angije mulkin Makau, wato sarautar Have ta asali a lardin Zazzau, ya kuma dasa mulkin Fulani, a cikin shekarun 1804 zuwa 1821.

---

[1] M.G. Smith, *Government in Zazzau*, (1800-1950), Oxford University Press, London (1960) shafi na 137-138

[2] *Ibid*. shafi na 138

Abin nuni a nan tare da jaddadawa, shi ne tun kafin jihadin Shehu, wato shekaru xari kafin zuwan Turawa, qabilu daban-daban sun zo sun tarkatu a kusa da dajin Doka da ke gavar kogin Kaduna. Kada a manta da cewa akwai Fulani a Barnawa da Sulluvawan Igabi, Hausawan Igabi da Afaka da na Maqera, tare da qabilar Gbagyi da ke Kakuri kurmin Gbagyi. Waxannan qabilu na zaman tare da taimakekeniya da juna. Amma tun a wancan lokaci na 'mai qarfi sai Allah Ya isa', waxannan qabilu ke zaune a qarqashin mulkin Zazzau. Haka kuma sun ba da gudunmawa gaya wajen ci gaban wannan lardi da Arewa baki xaya. Bunqasar garin Barnawa a wancan lokaci, misali ne babba. Saboda haka sai da Barnawa ta wuce shekaru xari tana mulkin wannan yankin kafin garin Kaduna ya xau hannu!

A Barnawa kuma, akwai Fulani Sulluvuwa da ke zaune a wannan gari a qarqashin Malam Kilba da xansa Abdulsalami. Shi kuwa Abdulsalami surukin Malam Musa Bamalli ne domin ya auri xiyar Malam Kilba. Mai yiwuwa ne ma saboda a daxa danqon zumuncin sararkuta ya sa ya naxa shi Makama da ya hau karagar mulkin Zazzau. Ana iya cewa ma wannan xa na Malam Kilba, shi ne ya zama Sarkin Zazzau ya kuma kafa gidan Sulluvuwa. To, idan wannan qaulin ya zauna daram da gindinsa duk Sarakunan Zazzau da suka kafa gidajensu sun halarci garin Barnawa. Malam Musa Bamalli da Malam Yamusa Babarbare da Malam Abdulkarim Bakatsine da Malam Abdulsalami Basulluve wanda za a iya kiran sa xan garin Barnawa ne.[1]

Malam Abdulkarimu ya riqe muqamin Sa'in Zazzau, a qarqashin mulkin Sarkin Zazzau Malam Musa Bamalli. Kuma ya yi shekaru goma sha-shida a Zariya kafin varkewar yaqin jihadi. Babu shakka ya halarci garin Barnawa garin amininsa Makaman Zazzau Abdulsalami. Su waxannan malamai da suka sami sarautar Zazzau ba sa gaba da juna kuma masu biyayya ne sau da qafa ga duk wanda Allah Ya ba shugabanci a cikinsu. Sun kuma dangane wajen tsoron Allah da adalci tare da son ci gaban jama'arsu.

Haka kuma a matsayinsu na malamai, su shugabanni ne masu neman ilimi a duk inda yake. Za su niqi gari su tafi garuruwa kusa da nesa wajen neman ilimi. Duk inda mavuvvugin ilimi yake sai sun qaru da shi. Saboda haka sai suka zama malamai masana fanni-fanni, ga kuma taqawa tare da adalci. Rokon Allah da shahidi Malam Muhammadu lawal ya yi tasiri sosai, Allah Ya azurta Zariya da mashahuran Sarakuna. Allahu Akbar!

A matsayin garin Barnawa na wani mavuvvugin ilimin addini wanda ya yi suna a wannan lokaci, sai ya zama wata cibiya kuma matattarrar maluma da shugabanni. Ana iya cewa kamar yadda garin Turunku ya zama cibiyar Sarakunan Have, shi garin Barnawa kuwa, shi ne cibiyar Sarakunan Fulani a lardin Zazzau.

---

[1] M.G. Smith, *Government in Zazzau*, (1800-1950), Oxford University Press, London (1960) shafi na 138

Su ne kuma suke mulki har yanzu an kuma sami Sarakuna goma sha-takwas daga zamanin jihadi zuwa yanzu, su ne:
Sarakuna daga Zamanin Jihadi

1. Malam Musa Bamalli (1804-1821)
2. Malam Yamusa Babarbare (1821-1834)
3. Malam Abdulkarim Bakatsine (1834-1846)
4. Malam Hammada Xan Yamusa (1846-1846)
5. Malam Muhammadu Sani (1846-1853)
6. Malam Sidi Abdulqadir (1853-1853)
7. Malam Abdulsalami Basulluve (1853-1857)
8. Malam Abdullahi Xan Hammada (1857-1871) da (1874-1879)
9. Malam Abubakar Xan Malam Musa (1871-1874)
10. Malam Muhammadu Sambo Xan Abdulkarim (1879-1888)
11. Malam Usman Yero Xan Abdullahi (1888-1897)

Sarkuna daga zamanin Turawan mulki

12. Malam Muhammadu Lawal Kwasau Xan Yero (1897-1902)
13. Malam Aliyu Xan Sidi (1903-1920)
14. Malam Xalhatu Xan Yero (1920-1924)
15. Malam Ibrahim Xan Kwasau (1924-1937)
16. Malam Ja'afaru Xan Isyaku (1937-1959)

Sarakuna daga zamanin mulkin kai

17. Malam Muhammadu Aminu (1957-1975)
18. Alhaji Shehu Idris, CFR (1975 har yanzu)[1]

Daga garin Barnawa sai kuma labarin Maqera wani tsohon gari wanda ya yi suna a zamaninsa. Asalin wannan gari ya taso ne daga Katabu, wato Mararraba Jos. A zamanin da wannan gari ke tashe a gavar kogin Kaduna, sai da ya zama wani babban cibiyar mulkin Zazzau, a matsayin garin na Hakimi.

Garin – Maqera

Wannan gari na Maqera ya kafu ne saboda fashewar jama'ar garin Maqera tsohuwa. Garin Maqera tsohuwa na Kudu da Zariya Gabas da Katabu. Garin a

[1] M.G. Smith, *Government in Zazzau*, (1800-1950), Oxford University Press, London (1960) shafi na 139

wancan zamani, babban gari ne, cike yake da jama'a. Ana jin wannan tsohon gari ya girme wa Zariya. A cikin shekarar 1800 A.D. ko kuma dab da hijirar Shehu Xan Fodiyo, an ce annobar ciwo ta varke a garin ta fasa jama'ar garin duk suka watse zuwa wasu 'yan garuruwa kamar Katabu (Mararrabar Jos) da Kangimi. Da yawa daga cikin waxanda bala'in annobar ya kora, sun yiwo Kudu zuwa bakin kogin Kaduna inda suka kafa gari Arewa, kaxan da Kakuri Kurmin Gwari. Mazauna wannan sabon waje sai suka zo da sunan tsohon garinsu, suka sa wa wannan sabon wuri "Maqera. "

Alhaji Aliyu Na Mangi ya kawo wannan tarihi a waqarsa ta Imfiraji don ya zama wa'azi ga ma'abota hankali. Shahararren mawaqin ya ce:

Ba a nesa ba ga Maqera,
Babu kowa sai fa Kura,
Sai karan-vuki shi ka qara,
Sai fa jam velvel da tsara,
Tamkar ba su tara 'yan-Adam ba.

Da garin sai masu iko,
yanzu ba ko masu tarko,
sai fa rimaye da vakko,
Soba mai son nuna fiko,
Baka samu ya su a mallaka ba.

Dandalinsu na cin abinci,
Babu kowa sai kumurci,
Xakunansu dila ka barci,
Da tana da riqon aminci,
Da jangwarzo ba zai mace ba.

Lallai, wannan abu da ya faru a garin Maqera tsohuwa, aya ce ga mai hankali. Allah Shi Ya halicci xan-Adam Ya kuma fifita shi bisa sauran halittunSa, sannan Ya karya shi da abubuwa uku; talauci da ciwo da mutuwa. Idan da babu waxannan abubuwa uku, to, da babu wanda zai saurara wa kowa, da kuma rayuwar xan-Adam ba ta amfane shi ba.

Garin Maqera nada gidan sarauta qarqashin Magaji Jisambo. A lokacin da aka yi sauye-sauyen muqaman gidan sarauta sai muqamin wannan sarauta ta koma ta Ubandoman Zazzau. Wanda ya fara riqe wannan sarauta shi ne Alhaji Sani Yaro. Bayan ya samu qarin girma, a lokacin da yake Galadiman Kaduna. Wannan hakimi ya rasu a watan Yuni na shekarar 2001 bayan ya daxe akan gadon sarauta.

A wannan lokaci sai aka naxa qaninsa Alhaji Aminu Tijjani Turakin Zazzau, wanda aka turo daga Ricifa don ya riqe hakimcin Kakuri. Shi ma Allah Ya yi masa rasuwa a ranar Laraba 31 ga watan Disamba 2003. A dalilin haka ne sai aka nada qaninsa Malam Shehu Tijjani Barden Kudu kuma Hakimin Kakuri a ran 31 ga watan Yulin shekarar 2004.

Garin Maqera sabuwa an kafa shi ne lokacin da Turawa suka fara aikin hanyar jirgin qasa, a shekarar 1911. Aikin wannan hanya ya bunqasa garuruwan da ke gavar kogi. A wannan lokaci ne kuma aka kafa Kakuri Hausa. Turawa sun samu tsohuwar Maqera da Kinkinau jama'ar waxannan garuruwa na qaruwa, su kan tsallako suna zaune a inda Masaqar *United* take. A wannan waje sai taruwar jama'a ta qaru kamar wani gari zai kafu, amma sai Turawa suka tashe su suka auna sabon garin Maqera suka dawo da jama'ar wannan wajen, a hankali, sai garin ya bunqasa cikin hanzari sai a ka fara turo wakili daga Zariya. An turo wakilai guda huxu: Magaji Inusa, Magaji Balarabe, Magaji Tabari Ibrahim da Iya Abdullahi. Shi Iya ya zauna a Kinkinau ne bai zauna a Maqera ba. Bayan shi sai Wambai, shi Wambai a Tudun-Wada ya zauna lokacin Tudun-Wada an gina mata Kotu da gidan Alqali. Bayan Wambai sai aka kawo Magajin Gari Sambo ya zama Hakimin Kaduna gaba xaya. Sai aka naxa Sarki a Maqera. Sarki na farko, shi ne Abubakar, Sarkin Maqera M. Ma'azu, Sarkin Maqera Shehu, Sarkin Maqera Dalhatu, Sarkin Maqera Alh. Umaru Ladan, Abubakar Yaron Ubandoma, har zuwa yanzu Sarakuna shida aka yi a Maqera.[1]

Kafuwar garin Maqera (sabuwa) a bakin kogi ya daxa bunqasa wajen. Mutanen wannan gari sai suka shiga sana'arsu ta noma da farauta da kamun kifi tun da yake yanzu ga su dab da kogi. A hankali sai kasuwanci da siyasa da sauran harkokin jama'a suka dawo kamar da. Akwai hulxar ciniki tsakaninsu da maqwabtansu kamar garuruwan Kinkinau da Kakuri Kurmin Gwari da Barnawa.

Saboda kafuwar alqarya a wannan gari da kuma tabbatar da zaman lumana ta fannin siyasa, sai maganar shugabanci ta qara qarfi. Da farko dai babu Sarkin Maqera sai Jakada. Ana naxa Jakada a matsayin shugaban Maqera daga Zariya, shi ke tafiyar da mulki tamkar Sarki. Akwai kuma muqamin Magaji Sambo a garin Maqera. Wannan muqamin na 'ya'yan Sarki ne ko kuma waxanda suke da jinin Sarauta daga Zariya, Majidaxin Sarki ke samun wannan muqami.

Garin Maqera ya bunqasa sosai lokacin zuwan Turawa. Aikin hanyar jirgi da kafa tashar jirgi sun havaka garin sosai, wajen samun qarin jama'a, ma'aikata da leburori. Arziqin jama'ar garin ya qaru saboda samuwar aiki da kasuwanci.

A zuwan Turawa, wanda ke sarautar, Magaji Sambo, shi ne Magaji Sambo Datti. Mai wannan muqami yana da iko da Maqera da sauran garuruwan da suke

---

[1] Kabir Zubairu, *Kundin Tarihin Garin Barnawa*

maqwabtaka da ita. Jakadan Maqera a wannan lokaci shi ne Ibrahim Muqaddashin Iya. Mulkinsa ba ya wuce Maqera.

Bayan rasuwar Ibrahim Muqaddashin Iya sai Malam Amadu ya samu Jakadancin Maqera. Dukkansu daga Zariya ake naxa su. Ta fannin siyasa, garin Maqera ya fi sauran garuruwan wannan wurin iko, saboda muqamin Magaji Sambo. Duk qananan garuruwan Gwarawa da ke Kudu da kogi suna qarqashin mulkin Maqera ne. Garin Gbagyi wanda ya fi suna da bunqasa a Arewacin kogin Kaduna ba kamar, Komi Namu, wata babbar tungar Gbagyi da ke kusa da Kurmin Mashi. A wannan gari a kwai zamantakewar Fulani da qabilar Gbagyi.

Kurmin Mashi

An kafa wannan gari ne a wajejen shekarar 1750, a lokacin da Fulani suka kwararo zuwa wannan shiyya. A wannan lokaci ne wani Bafilatani mai suna Aliyu Abubakar da xansa Usman Aliyu suka kafa ruga babba wadda ta bunqasa a qarqashin wannan dattijo, wanda Allah Ya azurta da 'ya'ya da dabbobi masu yawan gaske. Saboda haka sai ya zama shugaba mai faxa a ji, a sabili da haka ne sai Hausawa da Gbagyi suka riqa zuwa wannan waje don samun qasar noma da itatuwa. A wancan lokaci saboda wajen kurmi ne ana samun itatuwan gwangwala saboda haka sai wannan unguwa ta ci gaba da havaka cikin hanzari.

Ana nan sai wata rana wani maharbi Bafilatani Bakatsine ya zo ya sauka a wannan kurmi mai manyan itatuwan gwangwala saboda wajen na da namun jeji iri-iri masu yawa. Wannan Bafilatani Bakatsine sai ya sauka a wani kurmi a Yamma da titin *by pass* a yanzu. A wannan waje ne tare da jama'arsa suka zauna kusa da rugar shugaban wannan shiyya malam Aliyu Abubakar. A hankali sai wajen ya havaka. Saboda a sami qarin tsaro sosai sai aka kafa ganuwa a cikin surquqin wannan kurmi, inda jama'a ke da mahalli.

Zuwan wannan maharbi wanda yake xauke da Mashi da Kwari da Baka ya havakarda da wannan kurmi saboda ya kan fita daji a lokacin farauta duk naman dajin da ya harba ko ya tarar da shi a mace, to, sai ya soke shi da mashinsa. Saboda haka ne ake masa laqabi da "Mashi ", kurmin da yake zaune a cikinsa aka riqa kiransa "Kurmin Mashi. "[1]

Anan nan sai wani daga cikin jama'ar maharbin ana cewa da shi Mai Karauka ya fito daga cikin kurmi inda ya zauna a wani waje Kudu maso Gabas da wannan kurmi. A wannan waje ya kafa bukkarsa. A hankali sai jama'a suka riqa fitowa daga kurmi suna zama a wajen Mai Karauka. Nan da nan sai wannan waje ya bunqasa sosai saboda haka sai wani sabon gari ya tashi wanda ake kira Mai Karauka.

---

[1] Hira da Sarkin Kurmin Mashi, Alhaji Muhammadu Aliyu a ran 22 ga Agusta 2005

A hankali sai jama'ar tsohon garin kurmin Mashi suka riqa fitowa suna zama a Mai Karauka. Amma da wannan garin ya bunqasa sai ya xauki sunan tsohon garin mai ganuwa wato Kurmin Mashi. Kurmin Mashi gari ne wanda Hausawa da Fulani suka kafa suka yi masa ganuwa, babu wani garin Gbagyi da ya tava zama da su ko wata qabila a wannan lokaci.[1] Gidan sarautar Kurmin Mashi ta fi fiye da shekara xari uku da kafuwa, wanda ya fara shugabanci shi ne Aliyu Abubakar daga nan sai xansa Usman Aliyu.

A duk inda Fulani ke zaune suna maqwabtaka ne da Gbagyi a zamantakewarsu a wannan yanki. Akwai wuraren da qabilar Gbagyi suka kafa tungarsu kusa da Kurmin Mashi kamar Komi Namu. Daga wannan mazaunin ne suka tashi suka yi Yamma da Rafin Xinya. Har ila yau ana samun su a sassa daban-daban a Kurmin Mashi inda suke maqwabtaka da Fulanin wannan tsohon gari mai ganuwa.

Akwai Maguzawa masu aikin gwangwala da yin bammi a wannan waje tun kafin zuwan Turawa. A lokacin da hare-haren Nagwamatse ya tarwatsa Gbagyin yankin Neja sun kwararo zuwa Kurmin Mashi inda suka gauraye da Maguzawa wajen aikin gwangwala da sana'ar bammi. Haka aka yi wannan zama har lokacin zuwan Turawa inda sana'ar sayar da gwangwala da bammi suka bunqasa saboda qaruwar jama'a da gine-gine.

Kurmin Mashi gari ne mai albarkar qasar noma da itatuwan gwangwala da ciyawar dawakai. Saboda haka sai ya riqa samun baqi 'yancirani akai-akai waxanda suke zuwa suna aikin zana da sayar da gwangwala da ciyawa. Saboda bunqasar da yake yi sai hukuma ta lura sosai da shugabancin wannan gari mai albarka. A lokacin Magajin Gari Sambo ne gidan Sarautar Kurmin Mashi ta qara qarfi sosai.

Sai aka naxa Aliyu Usman Mai Unguwa a qarqashin Tudun-Wada kuma aka ba shi Galadiman Tudun-Wada. Ya yi shekaru ashirin da biyar yana Mai Unguwa. Allah Ya yi masa rasuwa a shekarar 1994, bayan shekaru ashirin da naxa shi Sarkin Kurmin Mashi daga nan aka naxa babban xansa Alhaji Muhammadu Aliyu Sarkin Kurmin Mashi na biyu a a shekarar 1994 zuwa 2001, lokacin da gwamnati Jihar ta yi qarin Hakimai aka naxa shi hakimin Kurmin Mashi, shi kuma ya naxa babban xansa Abduljalal Muhammadu Aliyu Sarkin Kurmin Mashi na uku daga a shekarar 2001 har zuwa yanzu. Amma a wancan lokacin in an tara haraji ana kaiwa Garin Afaka ne daga can su kai Zariya. Don dukkan garuruwan suna qasar Zazzaune, har lokacin da Turawa suka zo aikin hanyar jirgin qasa suka ga dajin doka su kai shawarwari kafa gari.[2]

---

[1] Hira Alhaji Muhammad Aliyu, Sarkin Kurmin Mashi, a ran 22 ga Agusta 2005

[2] Kabiru Zubairu, *Kundin Tarihin Barnawa*

Wani gari da ya shahara a zamaninsa, shi ne garin Rigacikun. Ko da yake wannan gari ba shi cikin yankin Kaduna, amma ya taimaka wa mazauna wannan gari a harkokinsu na kasuwanci da sauransu.

Rigacikun

A wajen shekarar 1835, waxansu mafarauta daga Kura ta qasar Kano, sun fito yawon farauta, amma sai suka sauka a wani waje da ke Gabas da garin Afaka. A wannan waje, sai suka yi 'yan bukkokinsu da xakuna, a hankali sai jama'a suka riqa zaunawa a wannan 'yar Unguwa. Jama'ar na nan zaune a wannan Unguwa, sai wani babban Malami Bazamfare tare da 'yan makarantarsa suka fito daga Bunguxu ta qasar Sakkwato. Sunan wannan Malami Yahaya Abubakar. Shi Malam Yahaya Abubakar da jama'arsa sai ya koma ya zauna a Unguwar da Kanawa mutanen Kura suka kafa, bayan ya zauna a Afaka da Ifira da wata Unguwa mai suna Unguwar Liman.

Zuwan wannan Malami da 'yan makarantarsa wannan Unguwa, sai ya bunqasa ta, ya buxe makaranta ya gina masallaci inda yake limanci. A hankali sai Fulani da Hausawa da kuma Gwarawa suka zo suka qara havaka Unguwar. Cikin xan qaramin lokaci sai Unguwar ta bunqasa. A kowace shekara mutanen wannan Unguwa suna hanzarin kai harajin qasarsu a Zariya. A wannan lokaci duk qananan garuruwan lardin Zazzau sai sun kai harajinsu ga Zariya a kowace shekara.

Ana nan a kowace shekara sai mutanen wannan Unguwa su 'riga' mutanen garin 'Cikun kai harajinsu Zariya. Saboda wannan halayya ta su sai aka sa masu suna 'Rigacikun.' Dalili kuwa saboda suna riga mutanen Cikun kai haraji. Liman Malam Yahaya Abubakar ya daxe yana limancin Rigacikun kafin xansa Malam Muhammadu Sani ya gaje shi. Shi Liman Malam Sani ya daxe yana limanci ya kuma bunqasar da babbar makarantar da ke wannan gari.

Kafin zuwan Turawa, garuruwan da ke kewaye da Dokar Dajin da aka kafa garin Kaduna guda huxu ne. Su ne: Barnawa da Kinkinau (ko Kangiwa) da Kakuri Kurmin Gbagyi da Kurmin Mashi. Duk waxannan garuruwa sun yi kusan shekaru xari da kafuwa kafin zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa. Haka kuma, duk waxannan tsofaffin garuruwan suna da ganuwa; mulkin Zazzau kuma na sane da su. Ta kuma san inda kowace qabila take da yadda ta zo, da lokacin da ta zo da inda take zaune. Haka kuma an san harajin da aka xora mata.

Tarihi ya nuna ba wani gari da aka tayar a Dokar Daji ko Doka, a lokacin kafa garin Kaduna. Abin dubawa a yanzu shi ne zuwan Turawa Arewa. Dajin doka waje ne da garuruwa suka kewaye shi musamman a gavar kogin Kaduna. Akwai garuruwa da suke Arewaci da Kudancin wannan kogi mai albarka, kamar yadda aka yi bayani. A wannan daji da turawa suka zo suka kafa wani sabon gari a ciki.

Abin da ya kamata sai a bayar da wasu dalilai da suka sanya Turawa shigowa Arewa har suka kafa wannan gari.

KASHI NA BIYU

Me ya Kawo Turawa Arewa?

Mulkin Kama-Karya

Mulkin zalunci da Allah Ya isa, an ce shi ya karya mulkin Sarakunan Have. Dalilin haka ne Shehu Mujaddadi ya yaqi waxannan miyagun Sarakuna, ya jaddada Addinin musulunci ya kafa mulkin adalci a qasar Hausa. A sababin haka ne mulkin Sarakuna Fulani ya taso ya raya qasar, ya kawo mata walwala da jin daxin jama'a, har mutanen wannan qasa suka yi fice a fannin ilimi da taqawa, da shahara wajen sana'a da bajinta a wajen yaqi tare da gogewa da qwarewa wajen sha'anin mulki. Jama'ar wannan qasa suka sami amincewar qabilu, Musulmi da waxanda ba Musulmi ba, har suka yi suna wajen gaskiya da riqon amana. Haka kuma jama'ar wannan qasa, suka shahara, suka zama abin koyi a nahiyar Afrika baki xaya.

Wani abin takaici sai mulkin Fulani ya shiga tavarvArewa, qasar Arewa kuma ta yi birgimar hankaka ta sauya zuwa hali irin na Sarakunan Have. Idan ba a manta ba, a cikin mulkin Sarakunan wannan lokaci, akwai mugunta da rashin adalci. Masu iko suke yin yadda suke so. Da mulkin Sarakunan Fulani ya tavarvare a kusan qarshen qarni na goma sha-takwas sai ya kusa yafi na Sarakunan Have muni da zalunci. A wannan lokaci ne Baraden Daular Usumaniyya, suka kaucewa tsarin mulki da Mujaddadi ya kafa ya kuma ba su wakilcin shugabancin Daularsa. "Ba kuwa abin da ya jawo al'amarin qasar nan ya zama haka, " in ji Abdulmaliki Mani, "Kamar savawar da manyan qasar nan suka yi, suka kaucewa ainihin irin hanyar adalci wadda Mujaddadi Shehu Usumanu xan Fodiyo da Muhammadu Bello suka nuna masu tun farko, " yaci gaba da cewa:

> *A kowace fada ta Sarakunan qasar nan, idan mutum ya je, irin mutanen da zai tarar su ne manyan barorin Sarki. Galibinsu kuwa masu mugun hali ne, marasa imani ko kaxan. Ba abin da suke yi sai aikata varna ta wajen yi wa talakawa marasa qarfi irin abin da bai kamata ba. Sai yadda suka ga dama suke yi kawai. To, su irin miyagun barorinnan na Sarakuna fa, ba su da mai hana su yin abin da suka ga damar yi. Hasali ma dai har a waxansu wurare sun kai ga raina shari'ar da alqalai ke yi, domin ko an kai su qara, sai ka ga Alqali tsoro ya hana shi zartar da hukunci tsakaninsa da Allah, tilas ya bi son zuciya ta su ko kuwa su yi masa sharri, ko su vata tsakaninsa da Sarki.*

Kuma wani mummunan abin da waxansu daga cikin barorin na fada ke yi, shi ne su riqa yi wa mutane azaba. Su kuwa sai su koma waje xaya suna murzar gashin baki, suna kallo, suna dariya, suna murna. Duk fiye da wannan kuma sai karvar rashawa da zalunci iri-iri suka zama jiki ko' ina a qasar nan." [1]

Da mulkin Sarakuna ya tavarvare sosai, sai ya koma mulkin kama karya. Wannan marubuci ya ci gaba da cewa:

Idan Sarki ya duba ya ga wata sana'a, ko wani ciniki, ko ma ya ga waxansu gonaki na wani waje sun yi kyau, sai ya tilasta su, su qara yawan kuxin abin da su kan ba shi a kan sana'ar nan, ko gonakin nan. Wajen qoqarin biyan jibgin abin nan da Sarki ya tambaya a biya shi, sai ka ga sana'ar, ko cinikin sun lalace, su qi ci gaba, har a qarshe su qare su bari xungun. Ba wai laifin Sarki ake so a nuna ba, a'a.[2]

Bari mu qara wata tambayar wadda amsa tata za ta sa mu gane lallai ba laifin Sarki ba ne shi kaxai. Shin Sarki ne da kansa yake zuwa wurin talaka ya ce masa ya kawo kuxi? A'a, abin nan an shirya shi mataki-mataki, har ma wataqila ainihin abin da talaka ya biya kafin ya shiga hannun Sarki, idan aka kasa yawan kuxin nan goma, to, da qyar Sarki zai ga kashi xaya. Domin sai jakadu sun amshi nasu tukuna sa'an nan su kawo wa Hakimai, su kuma su kawo masa nasa. A wannan lokaci kuma ba ruwan Hakimai da zaman lafiyana talakawansu, ko walwala tasu. Su Hakimai kurum sai su yi zamansu a fadar Sarki, su kima rawani su sha shuni kawai. Jakadun nan nasu su ne za su je su karvo kuxin, kuma su faxi dukkan umarnin da aka aike su da shi. To, jama'a kun sani fa ba zai yiwu duk abin da jakadun nan suka amso za su kawo ba, domin babu rasixi, babu wata shaidar da za a ce ga abin da suka amsa. Idan dai suka xebi abin da suka ga dama, sai su kaiwa hakimin da suke yi wa jakadanci sauran. Shi kuma ya zabgi nasa rabon, sa'an nan sauran ya kaiwa Sarki. "Lallai lokacin nan na kama-karya ya dace da a zo a gyara zaman qasar nan. Domin talakawa suna matse qwarai. Za su kuwa yi murna da kowane irin gyara aka taimake su da shi. Kuma attajiran qasar nan har ma za su

---

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na 17

[2] *Ibid*., shafi na 16-17

fi talakawan murna idan aka sami hana kama-karya, domin arziqinsu ya zama nasu. A zamanin nan na kama-karya, idan attajiri ya yi xan laifi, kai ko ma bai yi laifin ba, dare xaya sai ka ga an faxa masa an maishe shi mara kwabo. A yi masa wasoso, wato a wawashe gidansa bisa zalunci da fikon qarfi, ya zauna ba shi da komai kamar wanda ya yi gobara. Allah dai Ya yi mana tsari da sake dawowar irin wannan zamani, amin. [1]

Addu'a za ta taimaka, amma ba ta maganin zaluncin, wadda take halitta ce ta xan-Adam. Mutum mai son kansa ne, mai kuma son wanzuwa ne, saboda haka yake yin zalunci. Tarbiyya mai kyau ka iya rage zalunci amma ba ta maganinta. Babu kuma maganin zalunci da xan-Adam zai iya qirqirowa kansa, domin zalunci na cikin qoqon zuciyarsa ne, yana kuma gudana a cikin jininsa kamar sinadari. shari'ar musulunci ce kaxai maganin zaluncin da ke addabar rayuwar xan-Adam tun farkon wayewarsa har kuma qarshen rayuwarsa. Duk inda shari'a ta kafu, sai zalunci ya ragu, matuqar raguwa. Amma a duk inda shari'a ta yi laushi, ko kuma ba ta samsam, zalunci zai yi katutu, haka kuma darajar xan-Adam za ta faxi qasa warwas!

Alal misali, kamar yadda muka gani, a zamani Sarautar Have kusan a ce babu shari'a kwata-kwata. Amma a zamanin Daular Usumaniyya, a kuma lokacin ganiyarta shari'a ta yi qarfi sosai, saboda haka sai al'umma ta yi kyakkyawar rayuwa kuma abar misali a duniya. Domin zalunci ya yi matuqar raguwa. Ko a lokacin da mulkin Fulani ya shiga tavarvArewa, a na amfani da rubutu wajen tu'amuli da kuma wajen aikin hukuma. Ko da yake babu rasixi da ake bayarwa idan an biya haraji ko jangali, amma akwai gaskiya da riqon amana, waxansu halaye da ke hana algus da zamba cikin aminci. Ko a wannan zamani, wanda ya fi wancan zamani amfani da rasixi da boca da takardun shaidar mallakar filaye, amma duk da haka ba su taimaka wajen rage tafka almundahana a ayyukan gwamnati da na jama'a ba. A wannan lokaci ne ma ake amfani da rasixi da bocar bogi wajen tafka maguxi da yin sama da faxi wajen satar kuxin gwamnati ko na 'yan kasuwa.

Ba inda adalci zai wanzu sai inda shari'a ta kafu. Saboda ana ganin maganar zalunci ga shugabanni, aba ce da aka zata Turawa za su kawar cikin sauqi, wannan ya sa ake murna, lale da marhabin da zuwansu da farko. Har ma cewa aka yi: "Waxansu daga cikin Sarakunan qasar nan masu tsananin hangen abin da zai je ya zo, sun daxe da hango vacin sha'anin nan na kama-karya. Har a saboda

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa*, shafi na 16-17

tsinkayar nan tasu ce, suka yarda bisa lalama a game da zuwan Turawa, ba tare da an yi yaqi mai yawa ba. "[1]

Ayya, ai ba za a tsinkayi abin da ba ka san shi ba, ba ka kuma karance shi ba, ba ka kuma da wata masaniya da za ta nuna maka abubuwan ko dalilan zuwansu ba. Tunda ba ka da wani dalili qwaqqwara da za ka riqe a hujjar cewa in Turawa suka baro qasarsu, suka zo suka yaqi taka qasar, za su yi haka ne domin su kau da maku zaluncin da ke addabarku. An ce rashin sani ya fi dare duhu.

Amma idan kana xaya daga cikin masu "tsananin hangen abin da zai je ya zo, "waxanda suke da ra'ayin cewa, Turawa sun zo Arewa ne domin su ceto al'ummarta daga zaluncin shugabanninta, su kuma xora ta a kan turbar ci gaba, to, sai a ce har yanzu ba ka gama famfara ba. Turawa mutane ne masu zurfin ilimi, da hangen nesa, da kuma babban burin mallakar duniya baki xaya, domin kwashe arziqinta, saboda su sami rayuwa mai kyau da nishaxi tare da jin xadi. Haka kuma ba sa shiga al'amari, sai sun karance shi, sun kuma yi masa kyakkyawar fahimta. Duk da haka, sai sun xora abin kan mizanin riba ko faxuwa. Saboda haka suke masu qwazo da nuna bajinta wajen sayar da rai, a samo suna. Akwai dalilan da suka kawo Turawa Arewa, an san da yawa daga cikinsu ba kuma za a san dalilai masu yawa ba.

Turawan da suka shigo qasar Hausa sun rabu kashi-kashi, kowane kashi kuma yana da nasa dalilai. Amma duk waxannan dalilai ba su wuce na kawo ci gaban qasarsu da jama'arsu ba. A cikin Turawan da suka shigo Arewa akwai: Turawa 'yan Yawo, da Turawa masu Cinikin Bayi, da Turawan Mishan, da Turawan Kamfani da kuma Turawan Mulki. To, idan mutum yana maraba da zuwan Turawa, to, waxanne Turawan a cikinsu? Dukkansu sun haxa suna xaya, amma sun bambanta wajen manufa da dalilan da suka kawo su wannan qasa. Saboda haka sai ka san dalilin zuwan baqo kafin ka ce masa lale marhabun. Bari mu ji kaxan daga cikin rukunin waxannan Turawa:

Turawa 'Yan Yawo

Su waxannan Turawa suna yawo ne domin bincike da gano abubuwan da ke kan doron wannan duniya. Saboda a ko yaushe a kan sami mutane, musamman daga cikin jinsin Turawa, waxanda ke qoqarin sanin asirin komai. Akwai su da mutane masu son tafiya zuwa baquwar qasa. Tun da mutane ne masu burin mallakar duniya, sai ya zama wajibi a gare su da su san komai da ko'ina na wannan duniya. Alal misali, sun daxe da jin labarin kogin Kwara. Saboda haka a cikin shekarar 1795, sai wani likita daga qasar *Scotland* wai shi Mungo Park ya zo don bin kogin Kwara da niyyar gano masomin wannan kogi da inda ya qare.

---

[1] *Ibid.*

An ce tafiya mabuxin ilimi. A cikin shekarar 1821 Manjo Denham, da Leftana Clapperton, da Dr. Oundney suka fita qasarsu Ingila don su zo Kwara daga Turabulus. Da suka isa Kukawa ta qasar Barno sai El-Kanemi ya karve su da murna. Suka yi murna da ganin Tabkin Cadi daga nan suka zarce garin Kano. A wannan labari da C.R. Niven ya bayar ya ce: "Clapperton ya tafi Kano, ya yi shigan kaya irin na sojan jirgin ruwa na Ingila. Ko da yake shi ne Bature na farko da aka fara gani a Birnin Kano, amma mutanen garin ba su kula da shi ba. Bayan xan lokaci ya tafi Sakkwato, Sarkin Muslmi Bello ya karve shi da kyau… "Bello ya hana Clapperton ya ci gaba ya kai kogin Kwara a Yawuri. Ya ce sai ya koma da baya inda ya fito. Amma Bello ya ba shi taswira wadda ya ja da kansa, wanda ke nuna hanyar Kwara. Ya gaya wa Clapperton cewa wannan kogi iyakarsa a qasar Binis ne. ya cewa Clapperton ya turo masa likita da kuma wakilin ciniki su zauna a Sakkwato. " [1]

Sarkin Musulmi Bello, mashahurin mutum ne, wanda tun a wancan zamani har ya zana taswirar qasarsa ya kuma san amfanin yin haka. Wannan mashahurin Sarki, ya kuma san amfanin likita da muhimmancin qulla harkar diplomasiya da qasashen waje, musamman ta fuskar ciniki da kasuwanci da kula da lafiya. Saboda haka tunaninsa da iliminsa tare da hangen nesan sa, sun wuce na zamaninsa. Amma duk da haka ya tafi da zamaninsa ba tare da ya kawo wa jama'arsa abin da ya fi qarfin hankalinsu ba. Saboda haka har gobe, shi abin nuna misali ne, a harkar ilimi taqawa da shugabanci.

Akwai Turawa 'yan Yawo, masu yawa da suka shigo wannan qasa, waxanda suka kuma yaba da wayewa da ci gaban qasar Hausa wajen harkar mulki da sana'a da gogewa wajen hulxa da jama'a. Amma ba yawon buxe ido kawai suka zo yi ba, aikinsu ya haxa da na leqen asirin qasa. Su ne suka buxe wa Turawa masu cinikin bayi hanyar shiga wannan qasa. Wato kamar allura inda ta shiga sai zare ya biyo baya.

Tun zamanin da Turawa masu yawo ke shigowa qasar nan xaixai da xaixai daga qasashe daban-daban. Kamar Turawan Ingilishi da Faransa da kuma Portugal. Su ma Jamusawa ba a bar su a baya ba. Waxanda suka fi kusa da qasar nan ta hanyar teku su ne mutanen Portugal. Akwai dalilai daban-daban da suka kawo su nan. Xaya daga cikin dalilan zuwansu, inji C.R. Niven, shi ne Sarkin Portugal ya kan so jama'arsa su riqa fita suna zuwa qasashen duniya a jiragensu na ruwa. Yana so su gano masa yadda waxansu qasashen duniya suke, yana kuma so su kawo masa labarin sauran qabilun duniya.

Sun fara zuwa cikin shekarar 1472 daga qetaren teku. A cikin irin wannan tafiye-tafiye ne har mutanen Portugal suka isa Ikko, suka kuma xauki wannan wuri da muhimmanci, su ne suka ba garin suna "Lagos." Asalin wannan suna daga

[1] C.R Niven, "Labaran Nijeriya, shafi na .63-64.

"Lagoon " ne, wato hannayen teku. Mutanen Portugal suna kiran hannayen tekun nan, Lago di Kuramo, daga nan ne garin ya sami suna Lagos har zuwa yau.[1]

Mutanen Portugal sun kawo abubuwa masu amfani a qasar nan. Misali su ne suka kawo talotalo, da agwagwa da gwanda, da abarba da kwakwa. Duk waxannan tsuntsaye da itatuwa duka sun sami yanayin qasar ya dace da su. Ko da yake ba mu san abubuwan da suka kwasa suka kai qasar ba, amma Turawa 'yan Yawo sun taimaka wajen buxe kafofin cuxanya a tsakanin qasashe, sun kuma taimaka wajen musayar al'adu da fahimta tsakanin qasashe da suke nesa da juna. Turawan da suka biyo sawunsu, akwai Turawan cinikin bayi da Turawan kamfani.

Cinikin Bayi

Bauta wata tsohuwar sana'a ce da xan-Adam ya qirqiro wa kansa. A kusan dauloli goma sha-biyar da suka yi suna, a tarihin wannan duniya, bauta wata matsala ce da ke manne qut-da-qut da xan-Adam a tarihinsa a wannan duniya. Ita wannan muguwar sana'a, ta kaucewa tsarin musulunci, wanda shi ne Addinin qarshe. Irin wannan muguwar bauta, ta kaucewa koyarwar saukakkun addinai. Amma duk da haka Musulmi da sauran mabiya wasu Ibadu sun yi baqin suna a cikin wannan sana'a. Shigowar Turawa cikin wannan sana'a, a qasar nan ya assasa hare-haren kama bayi a cikin qabilu da kuma tsakanin qabilu. Saboda haka sai cinikin bayi ya zama kamar ruwan dare a sassa daban-daban na Afirka.

Abubuwa guda biyu sun tilasta Turawa su mamaye nahiyar Afirka. Na farko, shi ne qarin buqatar ma'aikata a Amirka da sauran qasashen Turai. Babu mutane da yawa saboda haka tilas a nemi ma'aikata a waje. Galibin ma'aikatan nan bayi ne waxanda aka kama wajen yaqe-yaqen da qabilun qasar nan ke yi. Saboda haka masu cinikin bayin nan suke sayen maza da mata suna zuba su a jiragen ruwa, su kai su qasashensu. Ana samun bayi qarfafa masu nagarta a qasar Hausa, saboda haka sai Turawa masu cinikin bayi suka juyo da hankalinsu zuwa wannan waje. Sababin haka ya qara assasa aikata yaqe-yaqe a tsakanin qabilu.

Kafin kace kwabo, hare-haren kamun bayi ya yi kusan ya zama annoba, saboda miyagun mutane masu saye da masu kamowa na samun riba sosai. Waxanda aka kama a kan aika da su bakin teku inda Turawa masu cinikin bayi ke jira da jiragen ruwansu, su saya su kwashe su, su kai qasashensu. Nagartar waxannan bayi da zaluncin shugabanni da kwaxaitarwar masu saye, sun haxu sun mayar da cinikin bayi babbar sana'a mai kawo riba mai tsoka. Amma wannan muguwar sana'a, sai ta faxi warwas da aka fara samun aiki da injuna da vullowar masa'anatu a Turai da Amirka. Saboda aikin da injin guda zai yi, a qaramin lokaci, ai bayi xari ba za su yi ba. Haka kuma zai fi sauqi xan kasuwa ya mallaki

[1] *Ibid*. shafi na 46

injin xaya fiye da bayi guda xari, saboda ciyar da su ma ai wani jidali ne. Domin haka ne sai aka himmatu wajen inganta hanyoyin samun injuna da bunqasa masana'antu.

Bunqasar masa'anatu, ta kawo wa qasar Hausa matsaloli biyu, wadda ita ce samar da kayayyakin masana'antu kamar tama da karfe, da *columbite* da zinari da makamantansu. Saboda samun waxannan kayayyaki masu daraja sai ya karkato da hankalin Turawan Kamfani, zuwa wannan wuri, musamman bayan an kashe cinikin bayi a qasar Turawa. Saboda arziqin wannan waje, sai Turawan Kamfani suka ce sun sami babbar kasuwa a wannan yanki saboda haka sai suka kwararo da farko a matsayin 'yan-ci-rani kafin su yi qarfi su zama Turawan Kamfani.

Turawan Kamfani

A shekarar 1877 wani jami'i injiya da ke *Royal Engineers* na qasar Ingila mai suna Mista Taubman Goldie (ya zama Sir) ya nuna sha'awar ya binciko wa qasarsa, nahiyar Afirka. Saboda haka sai ya shigo wannan nahiya tare da qaninsa ta saman kogin Nil, ya biyo ta kogin Kwara, ya kuma yi qorarin ya hayo ta saman kogin Binuwai. Amma bai sami damar yin haka ba saboda qaninsa ya kamu da rashin lafiya. Ko da yake wannan ya tilasta shi barin wannan shirin, amma sha'awarsa ga Neja da ya gano wannan yanki sai ya qaru. Ta dalilin haka ne, ya yi tunanin ya kafa kamfani, wanda zai buxe harkar ciniki a waxannan wurare, zai kuma baiwa qasar Ingila damar mallakar jama'ar wannan waje, inda za a kawo tsaro, da doka, da kuma kawo qarshen hare-haren bayi da yaqe-yaqe a tsakanin qabilun wannan waje.[1]

Matakin farko da *Tauman* ya xauka, shi ne haxe qananan kamfanoni da ke ciniki da kasuwanci a waxannan wurare, inda ya kafa wani babban kamfani mai suna kamfanin haxin kan Afirka wato *United Africa Company* (UAC). Bayan shekara da kafuwa, sai kamfanin ya sauya suna zuwa *National African Company*. Wannan kamfani ya bunqasa sosai ya kuma buxe harkokin kasuwanci a sassa masu yawa. Saboda qasaitacciyar nasara da ya samu da kuma taskar arziqi da ya buxe wa qasarsa, sai shugaban wannan kamfani ya samu qarin girma, ya zama Sir George Taubman Goldie.

Wannan Kamfani ne ya shiga wata yarjejeniya da Daular Usumaniyya a qarqashin Sarkin Musulmi Umaru. Ita wannan yarjejeniya ko da yake ta kasuwanci ce, amma sai ta zama musabbabin mallakar wannan qasaitacciyar Daula. Akwai yaudara da manaqisa a cikin wannan yarjejeniya wadda aka yi a ranar 1 ga Yuni na shekarar 1885. An xauki alqawurran cimma wasu sharuxxai, a

[1] Charles Orr, *The Making of Northern Nijeriya*, shafi na 18.

wannan yarjejeniya da ta share fagen Mulkin Mallaka a qasar Hausa. Ita wannan yarjejeniya an yi ta ne kamar haka:

Yarjejeniya Da Sakkwato

Akwai kwafi guda biyu na wannan yarjejeniya da aka yi a tsakanin Umaru na Sudan, kuma Sultan na Sakkwato, da shi kansa, da Sarakunansa, da Turawa masu kasuwanci a gavar kogin Kwara da Binuwai a qarqashin Kamfani mai suna *National African Company (Limited)*. An yarda da bin waxannan sharuxxa, kamar haka:

Sharaxi na 1: Domin amfanin kanmu, da jama'armu, da Turawa 'yan Kasuwa da ke qarqashin, *National African Company (Limited)*. Ni, Umaru Sultan Sakkwato na yarje wa wannan Kamfani, bisa shawarwarin 'yan majalisata, na kuma miqa wa wannan kamfani ko kuma waxanda suka baiwa izini, haqqoqin mallakar qasata gabaxayanta da ke gavar kogin Binuwai da hannuwan rafukanta da ke faxin daularta da kuma duk tsawon gavovin wannan kogi, kamar yadda suke buqata.

Sharaxi na 2: Mun kuma qara wa wannan Kamfani izinin yin kasuwanci a cikin baqin da ke zuwa wannan waje, mallaka da yin kasuwanci a duk yankunan waxannan wuraren da ake haqar dalma (lead) da kwalli (antimony).

Sharaxi na 3: Mun kuma yi alqawari da ba za mu yi tu'amuli da wasu baqi da za su zo ta teku ba, sai da izinin wannan Kamfani.

Sharaxi na 4: Mun xauki waxannan sharuxxaine a madadin kanmu da zuriyarmu da magadanmu har abada, mun kuma amince da ba za a warware su ba har abada.

Sharaxi na 5: Turawan wannan kamfani kuma wato *National African Company (Limited)* sun yarda da su riqa yi wa Umaru hasafi na kayayyaki waxanda kuxinsu zai kai buhunan wuri dubu uku wato "3,000 bags of cowries, " a sabilin sharuxxai da alqawura da aka xauka a wannan yarjejeniya.

An kuma sa hannu a kan wannan yarjejeniya a garin Wurno, a ranar 1 ga watan Yunin shekarar 1885. Wannan yarjejeniya na xauke da sahannun Sultan na Sakkwato (da Larabci) Da bugun hatimin Daular Usumaniyya. Shaidu a madadin *National African Company (Limited)* su ne: W.J. Seago, da D.Z. Viera, da T. Joseph[1]

Duk wanda ya dubi wannan yarjejeniya, zai ga babu adalci ko kuma niyyar yin adalci a cikinta. Zai kuma lura da cewa tana xauke da wata manaqisa ta ha'inci domin babu wata yarjejeniya da za a ce an shige ta "har abada. " Idan akwai niyyar yin adalci sai akwashi tsawon da yarjejeniyar za ta yi, na kamar shekaru

[1] Charles Orr, *The Making of Northern Nigeria*, shafi na 287

goma ko ashirin, kafin a sabuntata, ko kuma a kasheta kwata-kwata. A cikin sharuxxanta kuma sai aka sanya mallakar wuraren da za a yi kasuwanci har da wajen haqan ma'adinai, amma ba a tsaya a kan kasuwanci a waxannan wurare ba kawai. Aka xauki matakin da ya kange zuwan wasu baqin Turawa wannan waje kamar Jamusawa ko Faransawa ko kuma Turawan Portugal, saboda tsagwaron nuna babakere tare da handama.

A kuma wannan yarjejeniyar, Turawan Kamfani sun yi alqawarin bai wa Sarkin Musulmi hasafin kayayyakin da kuxinsu za su kai buhunhunan wuri 3,000, amma ba a faxi yawan wurin ko "cowries " da ke kowane buhu ba. Haka kuma ba a faxi darajar wuri a wajen canji ba, wato ko fam ko sulai nawa ke madadin waxannan buhunan kuxi ba. Ko shakka babu Turawan Kamfani ba su ba Sarkin Musulmi Umaru lokaci ya yi nazarin wannan yarjejeniya da sharuxxan da ta qunsa ba. Akwai yaudara a wajen gabatar da ita. Domin wannan ha'inci ne babba.

Da wannan kamfani ya samu wannan izini, sai a cikin shekarar 1886 gwamnatin Ingila ta ba su iznin su zama kamfani su kuma kira kansu *Niger Company*. Kuma su yi ciniki a wannan yanki na Neja. Kwaram! Sai ga 'yan kasuwa sun rikixe sun zama 'yan Mulkin Mallaka. Saboda haka sai wannan kamfani ya kafa xakunan shari'a, ya kafa 'yan Sanda, masu karvar haraji. Babbar cibiyar harkar wannan kamfani ita ce Asaba.[1]

To me ya kai 'yan kasuwa karvar haraji? Dalilin haka bai rasa nasaba da bambamcin niyya da fahimtar yarjejeniyar farko ba. Turawan Kamfani su na ganin sun yaudari masarautar Daulan Usumaniyya sun "Saye" gavar kogunan Kwara da Binuwai. Shugabannin Daula kuma suna ganin kasuwanci kawai Turawa za su riqa yi suna kuma kawo masu hasafi shekara-shekara. Ashe Sarkin Musulmi, ya taka ruvavviyar qaya ce bai sani ba.

Amma saboda garavasar da kamfani ya samu, sai ya bunqasa da hanzari, har gwamnatin Ingila ta qara masa girma, ya zama *Royal Niger Company*. Saboda haka sai suka sabunta yarjejeniyarsu da Daular Usumaniyya, a garin Wurno a ran 15 ga Afrilu na shekarar 1890.[2] An yi wannan sabuwar yarjejeniya da Kamfani mai suna *Royal Niger Company* a maimakon *National African Company*. Ita wannan sabuwar yarjejeniya ba ta bambanta da tsohuwar yarjejeniya ba, amma ta qara wa Turawan Kamfani ikon karvar haraji daga baqi da ka shigo wannan yanki. Amma kuma an cire batun baiwa Sarkin Musulmi hasafin kayayyaki. Daga qarshe Turawan Kamfani sun xauki duk matakan mallakar wannan wuri, da kuma yin babakere ga wasu baqin Turawa da ka shigo domin cin arziqin wannan yanki na Neja.

---

[1] Charles Orr, *The Making of Northern Nigeria*, shafi na 287.

[2] *Ibid*.

Turawan Kamfani na cikin handama da babakere Kwaram! Sai ga Jamusawa sun durkako zuwa wannan yanki suna neman a ci da su ido rufe, har sun bayyana a qasar Kamaru da qasar Togo duk sun zama mallakarsu, a shekarar 1884. Wannan abu ya tayar wa da sauran qasashen Turai hankali, ya kuma haifar da wawason kama wurare a tsakaninsu. Wannan wawaso kuma ya haifar da taron Berlin a watan Oktoba na shekarar 1884.

Wasoson Kama Wurare

Turawan Ingilishi, mutane ne masu hangen nesa, saboda haka sun tsinkayi zuwan wawason wurare tsakanin manyan qasashen, sun yi kuma yi masa kyakkyawan shiri. Wawason kama wurare a nahiyar Afrika da manyan qasashe suka yi, sai ya tilasta yin taro na musamman a garin *Berlin* hedwatar qasar Jamus, a watan Oktoban shekarar 1884. Wakilan manyan waxannan qasashe guda goma sha-huxu sun halarci wannan babban taro. An shirya wannan taro ne domin a tattauna abubuwa da dama game da nahiyar Afrika da yadda za su kasaftata ba tare da varqewar rikici a tsakaninsu ba.

Qasar Jamus da Faranshi, sai suka lura da kada su bari qasar Ingila ta tsere masu. Hasali ma dai su Faransi da Jamus har sun turo na su wakilan na musamman, don su zo su gayar masu da Sarakunan Afirka, tun daga Turabulus har Kamaru. Abu dai ya tsananta tsakanin manyan qasashen nan, har ya zamana yau sai Jamus su kafa tuta nan, su ce, "Mulkinmu ne! " Gobe kuma Ingilishi su kafa can, su ce, "Namu ne nan! "[1] Ta haka ne aka kasafta nahiyar Afirka, kowace qasa ta samu rabonta. Dukkan manyan qasashen nan suka himmatu ga kafa iyakar qasashen da aka xebar masu.

To, da ma a wancan lokacin har Turawan Kamfani sun fara ciniki da Ikko, da sauran qasashe da ke kudancin Neja. A wannan lokaci kuwa gwamnatin Ingila ba ta sa hannu a sha'anin waxannan wurare ba. Amma duk da haka sai mulkin wannan waje, ya zama kasonta, saboda aikace-aikacen Kamfani da arziqin da ke wannan yanki.

Sir Goldie Taubman, shi ne ya wakilci Ingila da kamfaninsa wato *Royal Niger Company* a wannan taro inda ya bayyana cewa duk harkokin kasuwanci da ke tsakiya da qasar Yankin Neja na hannun Turawan Ingila ne, akwai kuma wuraren da aka kafa tutar Kamfani a wannan qasa. A wannan lokaci an sami labarin cewa qasar Jamus, na qoqarin aikawa da jakadanta zuwa sauran yankunan wannan waje daga qasar Kamaru. Amma tun kafin hakan ya faru, sai aka yi wa tufka hanci da cewa tun wajen shekaru sittin da suka wuce, Clapperton ya kawo wasiqa daga Sarkin Musulmi Bello, wanda ya buqaci Ingila da ta buxe harkar kasuwanci da

[1] Abdulmalik Mani, *Zuwan Turawa Arewa*, shafi na 6

Daularsa. A dalilin haka ne Turawan Kamfani suka aika da wakilinsu domin ya shiga yarjejeniya da Daular Sakkwato a shekarar 1885.[1]

Shugabannin Daular Usumaniyya, tun daga Sarkin Musulmi Bello har ya zuwa Sarkin Musulmi Umar sun buqaci qulla huldar kasuwanci ne da qasashen waje ta hanyar cuxeni-in-cuxeka. Ko kaxan babu wanda ya tsammaci cewa za a yi amfani da wannan dama a angije wannan Daula da qarfin soja. Ko da yake kamfanin ya shiga yarjejeniyar kasuwanci ne da Daular Usumaniyya, amma sai gwamnatin Ingila, ta yi amfani da wannan dama ta shiga harkar siyasar wannan waje da Denham da Clapperton suka binciko har ya zuwa yankunan da ke gavar teku. Wannan niyya ce ta shirin mallakar Daular Usumaniya gaba xaya.

Sir Goldie ya yi amfani da wasiqar Sarkin Musulmi Bello, wajen gwagwarmayar mayar da yanki a Neja qarqashin mulkin Ingila, a wawason Afirka da manyan qasashe suka yi a shekarar 1884. Ya kuma yi nasara. Shi kuma Gwamna Lugga ya karvi mulkin wannan yanki daga hannun Kantin Kamfani a shekarar 1900. Ya yi kuma amfani da yarjejeniyar wannan Kamfani da Daular Usumaniya wajen kafa hujjar angije ta da qarfin soja, a Shekarar 1903.

Ko da Turawan kamfani suka zo, wannan yanki da sigar kasuwanci basu shiga harkar addinin jama'a ba saboda wannan haqqin Turawan Mishan ne.

Turawan Mishan

Turawan Mishan sun nuna zakwaxin son su buxe majami'u da wuraren watsa addininsu a qasar Hausa, musamman bayan da wannan yanki ya koma qarqashin Mulkin Mallaka. Amma sai aka so su xan dakata, sai an kammala haxa hanyar jirgi wanda zai taimaka wajen kawo tsaro, a waxannan wurare. Duk da haka sai da qungiyar *Church Missionary Society* (C.M.S) ta nemi izini da a bata damar kafa cibiyar yaxa Bishara, a wani garin Hausawa da ke mil arba'in, Kudu da Zariya a shekarar 1904. Da kuma izinin Gwamna, wannan qungiyar Mishan ta kafa cibiya a garin Zariya, a inda ta kama hayan wani gida a tsakiyar wannan gari. Amma kafin Gwamna ya ba su izini, sai da ya umarci Razdan na Zariya da ya tuntuvi amincewar Sarkin Zazzau, wajen kafa cibiyar Mishan a hedkwatar lardinsa, ya kuma bayyana wa Sarki da ce gwamnatinsa 'yar baruwammu ce a harkar addini. Ita wannan cibiyana aikin kula da lafiya, a cikin gari da kewaye, jama'ar gari kuma na ba su girma.

Shi kuwa Likita Miller, wanda yake cikin manyan Turawan Mishan, har ya riga Gwamna Lugga da sojansa zuwa qasar Hausa. Ya taho daga Ikko, a lokacin da ba a riga an ci qasashen Hausa ba, ya kuma yi mako shida yana tafiya kafin ya isa Kano, a lokacin Sarkin Kano Aliyu Babba. A wannan zuwan na su, Likita Miller ya ce, Sarkin Kano bai yi masu karvar kirki ba, ya kuma fito fili ya nuna

[1] Charles Orr, *The Making of Northern Nigeria*, shafi na 287.

bai yarda da su ba. Abubuwan da Turawan Mishan ke tinqaho da su, ba su wuce karatun boko da buxe wuraren shan magani ba. Saboda haka da Turawan Mishan suka sadu da Sarkin Kano sai suka yi taqaddama da shi:

"Da suka tambaye shi suna so su gina makarantu, ya ce a'a. Ya ce in dai makaranta ce, ai akwai makarantu, kuma irin makarantun nan ne a ke koya wa 'ya'yan jama'a karatun Alqur'ani. A game da maganar suna so su kafa asibiti kuma, Sarkin Kano ya ce, "Duk maganin da mu ke so akwai shi cikin Alqur'ani, da sunan Allah. "[1]

Har gobe ba wanda zai share wa Sarkin Kano Aliyu Babba zane, akan taqaddamar da ya yi da Turawan Mishan. Makarantun da yake magana akai, Makarantun Allo ne waxanda Sarakunan Arewa ke kula da su, suke kuma taqama da alfahari da su, a matsayinsu na manyan cibiyoyin koyar da karatu, da rubutu, da kuma haddar Alqur'ani Mai girma. Waxannan makarantu suna zaman kamar manyan cibiyoyi ne na yaxa ilimi a qasar Hausa, sun kumafidda mashahuran xalibai waxanda suka yi suna a duniya, shekaru aru-aru kafin Turawa kansu ya waye har su zo qasar Hausa. Saboda kyakkyawan tasirinsu a ci gaban qasar Hausa, ya sa Turawan Mulki su ka rusa su, suka tarwatse har ya zama ba su da madafa a qasar haihuwarsu a yanzu. Har kuma ya zama sai al'majiran waxannan makarantu sun rungumi qasqanci da barace-barace kafin su sami abincin da za su ci domin su ci gaba da karatun Alqur'ani. Duk wanda ya yi nazarin gudunmawar da waxannan makarantu suka bayar wajen ci gaban Arewa, zai yarda da Sarkin Kano Alu, lallai makarantu ne da za a iya taqama da alfahari da su. Amma da wannan mashahurin Sarki, zai dawo ya ga yadda waxannan makarantu suka koma a wannan zamani namu, zai ce, " Allah Ya Isa! " Saboda an ci amanar Makarantun Allo!

Haka kuma maganar cewa, "Duk maganin da mu ke so akwai shi cikin Alqur'ani, " ya dace da iliminmu da binciken da aka yi a kan wannan Littafi Mabuwayi. A taqaice dai tasirin wannan Littafi ne, ya baiwa duniya ilimin kimiyya da fasaha da ilimin magani na zamani da sauransu. In ba domin Alqur'ani Mai girma ba, da Likita Miller bai sami ilimin magani ba, domin da annobar cutuka iri-iri sun hallaka xan-Adam a wannan duniya. Saboda haka ne wani mashahurin Baturen Ingila mai zurfin ilimi mai suna Thomas Carlyle ya ce: "Zuwan Annabi Muhammadu (SAW) ga duniya rahama ce ga bil-Adama baki xaya. "

---

[1] Abdulmalik Mani, *Zuwan Turawa Arewa*, shafi na 23.

Daga qarshe dai Sarkin Kano ya sallami Turawan Mishan, ya ba su kwana uku da su shirya kayansu su bar qasarsa.[1] Ya kuma nuna adalci da ya ba su jakuna xari waxanda za su kwasam masu kayansu. Amma ko kaxan Likita Miller bai ji daxin abin da Sarkin ya yi masa ba, saboda haka bayan shekaru kusan hamsin ya wallafi littafi inda ya baqanta mulkin Sarakuna. Likita Miller, abokin Gwamna Lugga ne sun daxe suna tunanin yadda za su ci nasara a wajen yaxa addinin Kirista a qasashen Musulmi. Likita Miller ne ya yaqi shirin qarfafa Makarantu Allo wurjanjan, saboda a ra'ayinsa ka da a raba ilimin boko da yaxa addinin Kirista. An ce ma da Lugga da Miller sun yarda a kan abubuwa da yawa da su ka shafi ilimin boko da za a baiwa 'yan Arewa.[2] Miller bai voye tsanar da yake wa waxannan makarantu ba. Domin inda ra'ayin sa za a bi da an tarwatsa da qarfin soja. Da baqin cikin son haka ya bar wannan duniya wato kaska ta mutu da haushin kifi.

A harkar zuwan Turawan Mishan Arewa, Miss Miller wata mashahuriyar Baturiyar Mishan ta bayyana yadda al'amura su ke a da, a farkon shigowarta Arewa a shekarar 1907.

Yadda Al'amura Suke a da

Sananniyar Baturiyan nan ta Mishan, wadda a ke kira Miss E.P. Miller, ta yi magana a rediyo. A lokacin nan ne ta ba da labarin farkon zuwanta qasar nan, Miss Miller ta ce:

"Na tuna, na shigo Nijeriya cikin shekarar 1907 tare da waxansu Turawan mishan. Mu uku mata, tare da waxansu maza biyu – xaya lauya ne, xaya kuma mai wa'azi, parson. Ga mu kuma tare da bishop na Ikko kansa, tare da uwargidansa, shi ma ne shugaban tafiyar. Abin gwanin ban tausayi, sa'ad da muka baro tashar jirgi ta Liverpool. Bishop Chavasse, a gidansa muka yi kwana na qarshe kafin mu taso. Ya kuwa yi mana liyafa mai yawa, muka rabu, shi yana baqin ciki, mu kuma muna baqin cikin rabuwa da shi, ga kuma tafiyar da ke gabammu.

"Muka shiga cikin jirgin ruwa, cikin Kogin Neja zuwa Lakwaja, inda Sir William, sa'an nan yana Mr. Wallace xinsa bai sami darajar Sir ba. Shi ne yake Muqaddashin gwamnan Kamfanin Neja, kuma bai yi aure ba. Amma mu duka ya saukar da mu.

"Daga Lakwaja da muka tashi a qasa sai Bida. A can muka tarar da shahararren mutumin nan, wanda ya wallafa qamus na Hausa, Likita Bargery. A

---

1 *Ibid*.

2 Aliyu Dauda, *State Education in Northern Nigeria, First Edition*, gidan Dabino Pub. Kano (2002), shafi na 28.

cikin xan qaramin gidansa na ciyawa ya saukar da mu, mu wajen shida, ya ciyar da mu ya shayar da mu, muka yi hani'an.

"A Bida ne, ran safiyar Easter, ko da muka wayi gari sai muka ga duk leburorimmu da suka xauko mana kaya, qunshi 150, babu sauran ko mutum xaya, duk sun watse. Sun gudu saboda tsoron shiga cikin haxarin da za mu kutsa kai ciki wajen tafiyar da ke gabammu. To, a lokacin nan ne fa Bishop Tugwell ya nuna kansa, cewa lallai shi tsayayyen mutum ne, kuma Kirista babba. Kafin duk ya yi wani qoqarin shiryawa a xaukar mana kaya, sai da ya shirya mana jibi saboda murnar Easter. Idan aka ce kaya 150, sai a ji kamar waxansu kaya ne na jin daxi mu ke tafe tare da su. Amma kuma sai a tuna, cewa mu shida ne cikin tafiyar. Ba kuma irin duk abubuwan da mu ke buqata kaxai za mu xauka ba, har da abincin da za mu ci wurin tafiyar. Domin mai yiwuwa ne a yi shekara guda mutum bai sami wani abinci sabo ba. Sa'an nan kuma tilas mu xauki kuxi, wato kayan hurhure. Na tuna da wani qunshin kaya nawa, wanda ya bai wa bishop wahala kullum. Mutum shida suka xauke da shi. Qunshi ne, a cikinsa akwai basukurina na hawa, akwai keken xinki, wanda shi ne na farko ga zuwa qasar nan. Sa'an nan kuma ga 'yan tsummokaraina na saqa su a tsakanin waxannan qarafa. Sauran kayana xaya tak, shi ne wani xan akwati da na riqo nama a cikinsa.

"A lokacin nan Zungeru ita ce babbar hedkwatar Jihar Arewa, can gwamnati ta ke. An kuwa ji da mu qwarai da muka sauka a can. Gwamna Lugga shi ne mai masaukimmu.

"Bayan mun xan huta a nan sai kuma muka tasam ma tafiyar mil 200 a qasa. Mu yara-yaran na cikin ayarin, muka hau basukurori. Bishop ya hau doki. Na tuna a gidan Gwamna, a Zungeru ne, Manjo Festing ya haxa mini basukur xina. Kai, wannan mutum ya yi mini kirki. Na ji shi ran nan yana gunaguni, yana yi da mu, har yana cewa, "Wawaye, amma jaruman wawaye kuwa!

"Qungurmin dajin nan da muka ratsa mil metan, daji ne inda Sarkin Sudan na Kwantagora, Nagwamatse ke harin bayi. Nagwamatse shahararre ne matuqa wajen harin bayi. Daga baya Keftin Orr ya kama shi a bayan Birnin Zariya, a lokacin nan kuwa wana, likita Miller, yana zaune cikin Birnin Zariya. Bayan shekara kamar ashirin na ga Nagwamatse xin nan da idanuna, yana gayar da xan Sarkin Ingila, Prince of Wales. Sarki mai biyayya, mai amfani.

"Muka qetare Kogin Koriga, kusa da inda yake shi ne hedkwatar gwamnati a yanzu a Kaduna. A lokacin nan babu gidaje, sai dai akwai 'yan zakoki kaxan – ba irin zakokin nan da su ke cikin manyan gidaje masu kyau a yanzu a wurin ba."

"An shirya mana maraba babba a Zariya. Ba motoci salun ba, ko manyan motoci don su xauki kayan mu, a'a, wani abu dai da ya fi duk waxannan, wanda ba ma zan yarda in gwada shi da abincin da zan ci ba. A qofar Kudu ta Birnin Zariya, sai ga wani Bahaushe, malami, ya fito domin ya tarye mu. A cikin jama'ar

da suka fito tare har da wana. "Malam Fati, wanda daga baya ya taimaka wajen fassarar Linjila, kashe-gari bishop ya yi masa wankan shiga addinin Kirista, Baptism, tare da Audu, qaramin alhaji. Wannan shi ne farkon Hausawa su shiga addinin Kirista.

"Wata tara muna cikin Birnin Zariya, muna yin iyakacin qoqarinmu. Waxansu daga cikinmu rashin lafiya ya kama su, har ma xayammu tilas aka mayar da shi gida. Biyu daga cikinmu suka tafi Qasar Kuza, inda ba a daxe da fara aikin haqar kuza ba a Naraguta. Kuma sa'an nan ko mishi-mishin garin Jos babu.

"A lokacin da Gwamna Lugga ya bar Nijeriya zuwa Hong Kong, sai sabon Gwamna ya ce shi kam ba zai xauki alhakkin tsare duk haqqin matan Turawa da ba su da aure a qasar nan ba, domin rashin hanyar sufuri mai sauri. Na ce ai ni ina da xan'uwana yana nan, amma Gwamna bai amince da wannan dalili ba, sai aka aika da ni ta cikin Kogin Neja, tare da Likita Franci Wakefield muka koma gida, sauran mu biyun da muka rage cikin ayarimmu.

"Sa'ad da na sake dawowa Nijeriya, sai aka ajiye ni a Kudu. Na yi shekaru cikin farin ciki a Abeokuta, Oyo, da Ibadan. Ina iya tunawa, cikin manyan Abokaina, akwai su Bishop Phillips, Revs. Olubi, Ogunbiyi, Ransome-Kuti da sauransu. A lokacin nan ne aka yi babbar gobaran nan a Oyo, wadda ta qone gidan alafin, Sarkin Oyo, qurmus. Babu wanda ya san iyakacin abokaina, matansa, da suka qone cikin wutar.

"Ni ce na ke duba makarantar 'yan mata ta Mishan na C.M.S. a Ibadan. Na tuna sarai, wani Yamma, muka yi ta jiran Bishop Tugwell da uwargidansa, don shagalin Lahadi. Aka shirya musu wurin kwana, abinci, wurin wanka da su sauran kayan alatu, amma har zuwa qarfe goma na dare ba mu ga baqi sun zo ba. Da dare ya raba sai muka fid da zuciya kamar ba za su zo ba. Amma muna shirin kwantawa ke nan, can cikin talatainin dare, sai muka tsinkayi qyallin fitila. Ashe Bishop ne tafe, shi da matarsa sun yi tafiyar mil 15 a qasa, tun daga wurin da jirgin qasa ya lalace. Haka sufuri yake a zamanin.

"A cikin 1915 na koma Zariya, na shekara goma ina aiki cikin farin ciki a Mishan na C.M.S. Na tara mutane iri-iri a gidana na qasa a cikin Birnin Zariya. Ga tsohuwa, tukuf-tukuf, ga ciki (ban san yadda zan yi da ita ba) ita ce mata ta huxu, da xanta namiji, 'yam mata shida ko fiye, duk zan karantar da su in yi tarbiyyarsu. Waxannan sun sanya na zama cikin harka qwarai. Amma babban abin sha'awar, shi ne inda duk na shiga cikin gidaje kowa da kowa, maza da mata, duk suna gaishe ni, 'yan yara a titi da ganina sai ga isuwa, suna kirana Bismillah, domin ba sa iya faxin sunana sosai.

"Sa'ad da na bar C.M.S. Sai na ce lallai Kano nan gaba ita ce za ta zama qasaitaccen birni a Jihar Arewa. Sa'an nan kuwa ina Zariya. Mishan suna cikin matsuwa qwarai, sa'an nan kuma babu wani da zai xaure min gindi, amma fa

zuciyata tana nan daram bisa irin qullin da ke tare da ni. Kuma ina da amintaccen yaro, mutumin Kano. Na ce ya tafi can Kano, gidan ubansa, ya gina man xakuna na qasa, guda biyu, na ce masa ina nan tafe bayan mako uku. Qauyensu yana can mil takwas tsakaninsa da Kano, ta kan jakai ne kaxai a ke iya zuwa can. A lokacin da na sauka daga jirgin qasa, babu mutum, kuma babu jakai, sai daga baya na samu muka isa qauyen. Ga shi kuma ba ni da wani mutumin da zai taimake ni ya shirya mini gado, ko ya yi mini kwaf na ti, sa'an nan kuwa ga zafi ya yi yawa.

"Shekarata uku a qauyen nan. Mai gidana kuwa wani amintaccen Musulmi ne, malami, muka yi abota mai qwari, in ya xauko Alqur'aninsa yana nazari, ni kuma sai in jawo littafina na waqoqi, ba mu tava yin wani savani ba kuwa. Kullum ana murna da ganina idan na je wurin bikin aure, ko na haihuwa, ko ma jana'iza. A kan kuma kira ni qauyuka na nesa domin in gano marasa lafiya. Da xan maganin da na ke riqe da shi, na warkar da mutane da dama. Amma ko wane mutum na warkar, su mutanen suna zaton Sarkin Ingila zai ba ni £5 ke nan. In ba haka ba ta yaya na ke samun abincin da zan ci? ."

Xibar arziqin Arewa ya kawo Turawan Mulki zuwa wannan qasa mai albarka. Dalilin haka ne ya sa aka karve izninin kasuwanci daga hannun Turawan Kamfani, a farkon shigowar Turawan Mulki Nijeriya ta Arewa a shekarar 1900. Don haka ne kuma aka shimfixa hanyoyi na jirgi da mota domin sauqaqa zirga-zirgar sadarwa a wannan qasa. Amma hakan bai samu ba sai da aka kashe cinikin bayi, aka kuma ci wasu qasashen Arewa da yaqi. Turawan Mulki sun ingije Daular Usumaniyya a shekarar 1903. A ran 21 ga watan Maris na wannan shekarar sai Gwamna Lugga ya yi jawabi ga jama'ar Sakkwato inda ya yi masu tuni da wani tsohon alqawari, inda ya ce: "Kun sani tun da daxewa Turawan kantin kamfani sun yi alqawari tsakaninsu da Sakkwato. ya yi alqawarin abota da zama cikin aminci da yarda da juna. Turawan kamfani suka yi alqawarin za su riqa biyan 'yan kuxi, sun kuwa yi ta biya. To, shekaru uku da suka wuce gwamnatin Ingila ta aiko mutanenta don su karvi mulkin qasar nan daga hannun Turawan Kamfani, suka naxa ni na zama Gwamna.[1]

Wannan lokaci ne na mai qarfi sai Allah Ya isa. Alqawarin da ke tsakanin Turawan Mulki da Sakkwato kamar fa yadda aka yi bayani, yarjejeniya ce ta kasuwanci amma ba ta mulki ba. Saboda su waxannan 'yan kasuwa ba su mallaki Sakkwato ba, ballantana a zo karvar mulki a hannunsu. Ai abin da ya kamata shi ne, Turawan Mulki su karvi yarjejeniyar kasuwanci, amma a maimakon haka sai suka karvi mallakar qasar baki xaya da qarfin tsiya. Hankalin jama'a ya tashi sosai saboda zuwan wannan sabon yanayi mai firgitarwa. An san Turawan kamfani,

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, Shafi 126.

ban da kasuwanci ba sa shiga harkar addini ko sha'anin mulki. To, yanzu an karve mulkin qasa baki xaya, to me Gwamna Lugga ke tafe da shi? Don haka sai gwamnan ya sa aka fassara wa su Wazirin Sakkwato, da Galadima da Sarkin Gobir Umaru, da Marafa Maiturare da Sarkin Burmi, da Sarkin Zamfara, da Sarkin Kabi, a ran Alhamis 20 ga watan Maris na shekarar 1903, irin tsarin mulkin da ke tafe da kuma dukkan abin da ake buqatar su yi a nan gaba. Gwamna Lugga ya ce mu su:

"Ba za a sa baki ba cikin addininku, ko kuma kan, da yake shi ne shugaban addinin naku. Gwanatin Ingila ba ta tava karambanin sa kanta kan wani addini ba, ko haraji, ko hanyar hukunci irin na hana laifuffuka, waxanda yake maganar gwamnati ne, ban da kuwa addini."[1]

Gwamna Lugga bai cika wannan alqawari da ya xauka ba. Domin kuwa ya fito fili yana baiwa Turawan Mishan tallafin kuxi don su yaxa ilimin Boko da Bishara. A farkon zuwan Turawa, Mishan xin da ake kira *Church Missionary Society* (CMS) qarqashin shugabancin Dr. Miller, suna da makarantu biyu rak a Arewa, xaya a Loko, xaya kuma a Lakwaja. Bayan kamar shekara guda kuma, cikin 1901 sai ga waxansu Mishan da ake kira Toronto Industrial Mission sun zo, a qarqashin jagorancin Reverend Anthony. Gwamna Lugga ya ga za su yiwa qasan nan amfani, tun ma ba a wajen qabilun da aka samu ba su da addini ba. Tun a wannan lokaci ne, saboda ganin yadda suke taimako, Gwamna Lugga ya ba da shawarar lalle ya kyautu a rika taimakon Mishan daga cikin abinda gwamnati ke samu don yaxa ilmi.[2]

Saboda haka Gwamna Lugga ya ce "gwamnatin Ingila ba tava karambanin sa kanta kan wani addini ba, yaudarar Musulmi ya yi don kuwa babu qashin gaskiya a wannan magana. Da tallafin quxi da yake baiwa turawan Mishan ne qungiyoyinsu suka kafu a Arewa sosai. A shekarar 1906 waxansu Turawan Mishan da ake kira *Mennonite Brethren in Christ* suka zo suka zauna a Shonga cikin qasar Ilorin. Daga su kuma sai Mishan xin da ake kira *Sudan United Mission* suka zo suka zauna a qasashen arna na Muri da na Bauci.[3]

Wani babban abin da jama'a ke tsoro da taraddadi shi ne yadda za su kare addininsu. Don kuwa a duk faxin Arewa kowa tsoro ya kama shi, jinin kowa ya

---

1 Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*,*Ibid*., Shafi shafi na 124.

2 *Ibid*., Shafi 267 - 268

3 *Ibid*.

kai ga akaifa. Muddin aka ce za a tilasta su bin addinin Kirista wato a riddatar da su, to a shirye suke su yi shahada baki xaya. Idan da riddar da su zai samu ba tare da wata matsala ba, to, da Turawan Mulki sun yi. Don su kashe tsuntsaye biyu da dutse xaya. Su kwashi arziqin qasa su kuma riddatar da jama'a. Amma saboda tsoron kada a vata biyu xaya ba ta gyaru ba, sai suka bar maganar addini, suka koma ga mulki da kasuwanci. Duk da haka ta ciki na ciki. Manufofin gwamnatin mulkin mallaka da Gwamna Lugga ya bayyana wa Shugabannin Daular Usumaniyya sun haddasa takun saqa tsakanin Turawan Mulki da Turawan Mishan a kan yadda za a mallaki Arewa.

Takun Saqa

Su Turawan Mishan ba haka suka so ba. Abin da su ke son gani shi ne duk inda allura ta shiga, to baqin zare ya biyo baya. Wato a lallasa masu qasar su zo su dasa addininsu. Da farko Gwamna Lugga ya so ya yarda da haka amma saboda shi mutum ne mai hangen nesa, sai ya fahimci cewa yin haka ba zai haifar da xa mai ido ba. A wannan lokaci akwai Dr. Bingham da Dr. Kumn da Dr. Miller, wasu manyan Turawan Mishan da ke qokarin yaxa aikin Bishara a Arewa.[1]

Gwamna ya san manufofin Turawan mishan, har ma an ce shi ne ya shawarci likita Bingham da ya kafa gidan mishan na *Sudan Interior Mission* (S.I.M), a tsakiyar Musulmi a Pategi a shekarar 1900.[2] Wata qila gwamnan ya yi haka ne don a gwada a gani in zai yiwu. Domin ya canza ra'ayinsa bayan ya yi wa Sarakunan Sakkwato alqawarin ba zai yi katsalandan a harkar addinin su ba. Domin haka ne Turawan Mishan da dama suka bayyana ra'ayoyin su a kansa, wasu su yaba wasu kuma su yi zargi. Bishop Tugwell na C.M.S ya ce shi a ganinsa, Lugga matsoraci ne har ya qara da cewa shi sam bai amince da irin mulkin Lugga da ya yi a Arewa ba. Dalili kuwa shi Tugwell ya so Turawan mishan su kai bishara ko'ina a kowane lungu na Arewa. Amma sai Lugga ya ce faufau, kada wani Baturen mishan ya riga sojojin Lugga isa wani gari. Idan kuma suka je, inda ba a yarda da su ba, har ya kai an kashe xaya daga cikin Turawan mishan xin, to tilas ne ya hori garin nan da qarfin soja, shi kuwa ba ya son haka.[3]

Wannan abin da Turawan Mishan suke son gwamnan ya yi ya kaucewa dalilin shigowar Turawan Mulki Arewa. gwamnan kuma yana yi masu da nunin cewa tunda ya yi wa Sarakunan Arewa alqawarin gwamnatin Ingila ba za ta yi shisshigi ga addininsu ba su su bi sannu. Don haka idan Baturen mishan ya je wani garin da

---

1 Musa Haruna, *Addinin Kirista a Qasar Jaba Da MaQwabtanta*, shafi na 35.

2 *Ibid*.

3 Musa Haruna, *Addinin Kirista a Qasar Jaba Da MaQwabtanta*, shafi na 35 – 36.

Sarkin bai yarda da zamansa ba, sai kawai ya kwashe kayansa ya wuce. Domin "Ni, " inji Lugga, "ba zan zaunar da shi dole a garin da qarfin soja ba. "[1]

Haka dai Gwamna Lugga ya riqa takon saqa da Turawan mishan, har ya tafi aiki a qasar Hong Kong. A shekarar 1906 Sir Percy Girourd ne ya maye gurbinsa. Shi ma sai ya shiga xauki ba daxi da Turawan mishan. Amma da zuwansa sai ya yi wa tufka hanci, ya sanya qa'idoji da dokoki da za a bi don a samu zaman lafiya da cimma muradi. Ya kuma assasa tsarin mulki ta kan Sarakuna wato *Indirect Rule* da Gwamna Lugga ya kafa a Arewa. A ganin Sir Girourd, Lugga kai tsaye yake mulkin Arewa, wato ya qwacewa Sarakuna Mulkinsu. Saboda haka sai Sir Girourd ya qara wa Sarakunan qarfin iko kamar yadda tsarin mulkin *Indirect Rule* ke buqata.

Gwamna Sir Percy Girourd ya sha samun suka daga Turawan mishan. An ce a cikin shekaru biyu da ya yi a mulki, ya kawo dokoki da qa'idoji iri-iri na hana Turawan mishan walawa a Arewa. Har ma cewa aka yi, ya yi iyakacin qoqarinsa ya rufe aikin Bishara gaba xaya a Arewa. Amma duk wannan zargi ne maras tushe saboda masu wannan zargi ba sa la'akari da yadda al'amuransu ke a wancan zamani. Haka kuma ba a bambanta abubuwa masu kyau da abubuwa masu yiwuwa ba. Ko da yake Girourd kamar Lugga ya yi imani cewa ayyukan mishan masu kyau ne amma ba masu yiwu ba ne a Arewa.

Domin ganin yadda Turawan mishan ke fafutukar neman dama al'amura, sai Turawan Kamfani suka vara suka kai qara Ingila.[2] Saboda haka sai 'yan kasuwa a Ingila suka mara wa Girourd baya suka ce ko kaxan ba su so a kawo Bishara a qasashen Arewa. Don Kuwa sun san ba abu ne mai yiwu ba. Za a vata biyu ne xaya ba ta gyaru ba. An yi amfani da gwamnatin Ingila don ta fahimci irin barazanar da Turawan mishan ke wa cimma nasarar xibar arziqin Arewa. A wata jaridar 'yan kasuwar John Holt an rubuta cewa: "A fitar da wannan Bishop Tugwell daga Niger. Don me za a bar shi, tare da Lugard suna kunna wuta (wutar tashin hankali) a Nijeriya ta Arewa? "[3]

Turawan mulki sun fi kowa sanin cewa tuge Addinin musulunci da kafa addinin Kirista a qasar Musulmi ba abu ne mai yiwuwa ba, musamman a qasaitacciyar qasa kamar ta Arewa. Don haka ne sai suka duqufa wajen kwasar garavasar arziqinta. Turawan Mulki sun san addinin Kirista sosai sun kuma yiwa Addinin musulunci kwakkyawan fahimta. Don haka ne sai suka ga musulunci ya fi dacewa ga jama'a. Wannan ya sa ake faxin cewa Turawan mulki sun yi iyakacin

---

1 *Ibid*. shafi na . 36

2 Musa Haruna, *Addinin Kirista a Qasar Jaba Da MaQwabtanta*, shafi na 35 – 36.

3 Ibid., shafi na 37

qoqari su zavar wa mutanen Arewa irin addinin da za su bi. Har ma cewa suka yi a ganin su, musulunci ya fi dacewa da talakawa 'yan qasa wato *Native Subjects*.[1]

Akwai dalilai masu yawa da su ka sa Turawa suka fifita Addinin musulunci bisa addininsu na asali. Na farko sun shigo Arewa sun sami tsari da harsashin ci gaban xan-Adam ta kowace fuska. Wannan abu ya ba su mamaki da sha'awa. Na biyu, sun sami rahoto sun kuma gani a zahiri cewa 'yan Arewa mutane ne masu gaskiya da riqon amana. " Sun yi tu'amuli da su, sun kuma jaddada gaskiyar wannan batu. A kuma hulxarsu da qasashe a Afirka da Asiya, 'yan Arewa sun yi ficewajen jarunta, da qwazo da mutunci. Wannan ya sa gwamnan Arewa na farko, Sir Bryan Sharwood Smith ya cewai abotar Nijeriya da Ingila mai xorewa ce kuma abokai ne a koda yaushe, wato *But Always as Friends*. Dalili na qarshe, shi ne lurar da Turawan mulki suka yi ta ganin cewa addinin Kirista na sanya jama'a yin bore a kan kowane tsari. Gwamna Lugga ya tava cewa wata qungiyar Mishan a shekarar 1904, da kada su yi wa 'yan qasa Baqar Fata wa'azi dai-dai da da Bature, a wancan zamani. Ya ce ko da shike gaskiya ne dukkanmu dai-dai muke a gaban Allah, amma duk da haka, idan xan qasa ya gane dai-dai yake da Bature, to mai yiwuwa ne ya yi wa Bature bore. Amma maimakon irin wannan koyarwa, Lugga ya ce, yafi so, "Turawan mishan su fi ba da qarfi wajen koya wa jama'arsu halin biyayya, da faxin gaskiya da aiki tuquru tare da taimakon juna. "[2]

Ko da yake Addinin Kirista na kawo wayewa da neman 'yanci amma babban abin da Turawan mulki ke tsoro da shi, shi ne yana assasa butulci da fajirci, abubuwan da Turawan ke matuqar qyama. Sun sha nuna misali da mutanen Kudu waxanda suka karvi addinin Kirista hannu biyu, suka kuma qarvi halayen Turawa suka yi watsi da nasu. An kuma fifita su bisa 'yan Arewa. Amma abin takaici sai ga su a kan gaba wajen korar Turawa da sunan neman mulkin kai, ido rufe. Sai kuma suka xana wa Turawa karan tsana saboda zalamar neman mulki wanda ya kai su ci da zuci. "Ba addinin Kirista ba ne ke sa mutane yin tawaye, halaye da xabi'un Turawa ne ke kawo muggan halaye iri-iri. A wancan zamani an haxa addinin da waxannan halaye na Turawa. Kada a manta da cewa addinin Kirista na koyar da son maqiyi da rama alheri da mugunta, da idan aka mari mutum a kuncin dama to ya miqa na hagu. A wancan zamani kuma Turawan Mishan da Rev. Bargery su ne kan gaba wajen taimakon gajiyayyu da taimakon marasa lafiya. Ana iya nuna misali da irin ayyukan ci gaba da Rev. Bargery ya yi wa Arewa.

Reverend Bargery

---

1 *Ibid*. shafi na 38

2 Musa Haruna, *Addinin Kirista a Qasar Jaba Da MaQwabtanta*, shafi na 46

Jihar Arewa ta yi bankwana da wani tsohon aboki wanda ya sadaukar da kansa xungum wajen yin aiki ga jama'arta. Shi ne kuma Baturen da ya shiga Nijeriya kafin Gwamna Lugga ya angije Daular Usumaniyya, a shekarar 1903. Har ila yau, shi ne Baturen farko da ya fara zama a Birnin Kano. Wannan mashahurin mutum kuwa shi ne Reverend G. P. Bargery.

Reverend Bargery ya kammala karatunsa a Jami'ar London a shekarar 1900 sai ya shiga cikin Qungiyar Abokai ta Cocin *Church Missionary Society* (CMS) domin aikin yaxa Bishara. Duk da haxarin da Turawan Mishan ke fuskanta a Arewa, a wannan lokaci wannan bature ya nuna dauriya wajen zama a Arewa, qasar da yake sha'awar yin aikinsa.

A shekarar 1910 ya yi fama da rashin lafiya har ya koma gida amma bayan shekaru uku sai ya dawo Nijeriya a matsayin Jami'in gwamnati mai kula da harkar ilimi wato *Government Education Officer*. Ya samu shekara goma sha-takwas yana karkaina a qasashen Hausa, inda yake nasari da koyar da harshen Hausa. Saboda cikin 'yan shekaru kaxan sai ga shi ya zama wani mashahurin malamin Hausa kuma hukuma a wannan fili. A wannan lokaci kuwa harshen Hausa bai fito fili ba sosai.

A shekarar 1922 ne gwamnatin Nijeriya ta karvi shawarwari da tsohon Gwamna Sir Hugh Clifford ya bata da ta baiwa Dr. Bargery aikin wallafa qamus na Hausa. Ana ba shi wannan aiki sai ya duqufa ka'in da na'in wajen yin wannan qasaitaccen aiki. A shekarar 1934 ya wallafa wannan littafi mai nauyin laba huxu kuma xauke da kalmomi dubu hamsin da biyu (52,000 words), wanda maxa'bar *Oxford University Press* ta xauki nauyin buga shi, a farashi sulai ashirin da biyar.

A cikin gabatar da littafinsa da aka, a buga a shekarar 1951, Dr. Bargery ya ce:

"Ya share shekara biyar wajen kammala wannan aiki a Nijeriya. Akasarin waxannan shekaru kuwa an yi su ne a Birnin Kano da Katsina tare da ziyarar garuruwa kamar su Daura, da Gumel, da Haxeja da kuma wasu qasashen da ke qarqashin mulkin Faransai, harda Gobir. An xauki ma'aikata Hausawa wajen yin wannan aiki daga Sakkwato, da Zariya da sauran qasashe.

"Ya kuma gode wa Canon Charlse H. Robinson wanda ya rubuta qamus, da aka fara bugawa a shekarar 1899 da kuma Farfesa D. Westermann wanda ya ba da gudunmawarsa ta gabatar da wasu abubuwan lura akan Hausawa da harshensu."

Bayan ya kammala aikin littafin qamus sai aka aika da shi Ingila don buga shi. gwamnati ta bada littafin a kan kuxi fam dubu goma sha-xaya (£11,000). An kuma karvi littafin a matsayin kundin bada digirin likita a fannin rubuce-rubuce. Littafinsa ya yi tasiri sosai don kuwa kowane Jami'i na Jiha ko na Tarayya yana

da kwafin wannan Qamus na Hausa a gidansa. Bayan kammala wannan gagarumin aiki ne, sai mawallafin ya yi ritaya, inda ya xauki muqamin Malamin Hausa a makarantar *School of Oriental Studies* da ke Jami'ar London. An sake dawo da shi Nijeriya ta Arewa a shekarar 1953, domin yaci gaba da yiwa gwamnatin Ingila aiki da wata qungiya mai sauna *Foreingn Bible Society* domin ya yi bitar fassarar Sabon Alqawari wato *New Testament*, cikin harshen Hausa.

A shekarar 1957 ne aka karrama wannan mashahurin mutum da lambar O.B.E. Ko da yake bai kammala aikin fassara Sabon Alqawari ba, amma duk da yana da qarfi da kuzari sosai a wannan lokaci da yake da shekara tamanin da biyu da haihuwa. Amma yana da matsalar ciwon haqiya saboda haka sai ya koma Ingila don neman magani. Ya bar aikin fassarar a hannun mataimakinsa, Mr. C. Sanderson.

Za a daxe ana tunawa da shi saboda gudunmawar da ya baiwa Jihar Arewa da kuma bunqasar harshen Hausa. Ya samu kusan shekaru hamsin a wannan qasa saboda haka ne ya san tarihinta sosai, musammn Jihar Arewa. A dalilin haka ne ma ya kan bada wasu tsofaffin labaran wannan jiha, a duk lokacin da yake zantawa da jama'ar da suka kai masa ziyara. Alamisali, a wancan zamani da ba a fara amfani da tsabar kuxi ba, da Wuri wato *Cowries* ake amfani. Akan ajiye Wuri cike a buhunan ne. Idan za a sayi akuya akan wari dubu biyu da xari biyar (2,500), ba zama ake yi a qirgasu ba, akan bayar da buhunan da aka san yawan wurin da ke ciki. Akan kuma sake qirga dubban wurin da ke cikin kowane buhu a lokaci lokaci. Haka kuma a wancan zamani babu hanyoyin mota a wurare, sai a qasa ake tafiya ko kuma bisa raquma da jakai.

A gida mai lamba, No. 7 Park Lane a birnin Kano ya zauna. Ya maida Kano gida, ya kuma shaqu da wannan birni sosai. A lokacin da yake wallafa qamus na Hausa, a cikin birnin Kano ya tare da zama. Amma da ya lura da ana qyamarsa, ba a kuma ba shi haxin kai sosai, sai ya koma birnin Katsina, inda aikinsa ya samu ci gaba sosai. Amma daga baya ya fahimci dalilin da ya sa ake qyamarsa a birnin Kano. A lokacin Sarkin Kano na zargin an turo shi ne ya yi aikin leqen asirinsa da jama'arsa. Saboda haka ne bai samu goyon bayan da yake buqata ba.

Nijeriya ta Arewa ta yi wa wannan mashahurin mutum bankwana a lokacin da zai koma gida xungum, ya koma garinsa Exter da ke Ingila. Ko da yake ya shafe shekaru masu yawa yana aiki a Nijeriya amma duk da haka bai yanke dangantaka da garinsu ba. Don haka ya koma gida cikin murna da farin ciki. A lokacin da yake wa Arewa adabo ya shaidawa jama'a cewa babu wani abu takamaimai da zai tuna saboda duk a zamansa da ya yi a Arewa abar tunawa ce. Kafin ya shiga jirgin qasa zuwa Ikko a matakin farko na komawarsa gida sai da ya ce yana fata wannan bashi ne ritayarsa ta qarshe ba.

Turawan mulki sun riga Turawan mishan shigowa Arewa. Saboda tasirin Mulkin Mallaka ya sa za a yi bayani a kan zuwan Turawan Mulki daga farko. Za a fara da cewa maraba da baqi.

Maraba da Baqi

Sir C. R. Niven masanin tarihin Nijeriya, ya bayyana wasu dalilai da suka kawo Turawa Arewa. Ya ce mutane suna tafiya a kan qasar nan ne, amma tafiya a kan ruwa sai cikin kwale-kwale ko jirangen ruwa. Ta jirage Turawa kan shigo qasa a kan Kwara da *Cross Rivers* a cikin jiragen wuta. Me ya kawo su? Ka san maqwabtanka su kan zo ciniki da jama'ar wannan qasa. Haka ma fararen mutane ciniki ke kawo su daga qetaren teku, wato don "musaya " ko "furfuren " hajja. Suna buqatar kayan qasar kamar *Cocoa*, mai, kaxanya ko kuza. A maimakon waxannan su kan kawo irin kayan da a ke so a Nijeriya: abinci, tufafi, mashin da sauran kaya wanda injin ya yi.

Mutane su kan ji daxin zama, idan cikin kowace ma'amala akwai gaskiya. Amma su waxannan baqi sai suka zama ban da ma kayan qasar har mutane maza da mata da yara duk suna so su saya, su kai su qasarsu don su yi masu aiki a gona. Kun dai ji labarin wannan mummunan ciniki da a ke kira cinikin bayi.[1]

To, ana cikin sana'ar bayi, sai manyan Turawa, masu tsanani, masu tausayin jama'a, suka tashi tsaye suka yi ta wa'azi, suna qarfafa cewa addini fa ya hana irin wannan ciniki. Saboda haka sai hukumomin qasar Turai suka yi taro a garin *Utrecht* ta qasar *Holland*, a shekarar 1807, inda suka yi alqawari, su duka suka sa hannu a kan cewa sun yarda da a hana cinikin bayi.[2]

Kayayyakin gona iri-iri sun yi kasuwa a lokuta daban-daban kuma Nijeriya ta yi alfahari da su. Ko da yake yanzu arziqin gona ba shi da kasuwa kamar da, saboda samun kayan ma'adinai kamar man-fetur da tama da qarafa da sauransu, amma duk da haka dole tarihi ya kawo amfanin da suka yi wa wannan qasa tun fil-azal, wato tun kafin a fara tinqaho da kayan ma'adinai.

Don fahimtar yadda arziqin qasa ke sauyawa da zamani sai mu nitsa, mu kuma zurfafa cikin tarihi, mu faro tun zamanin da ba a haifi qasa mai suna Nijeriya ba; wato tun ana kiran wannan wuri da yankin Neja wato *Niger Area*.

Rahoton samun auduga da aka ce akwai ta jingim a garin Abeokuta da ke Yammacin Nahiyar Afirka da ke yankin Neja, ya jawo hankulan manyan qasashen duniya, Ingila da Amirka zuwa ga wannan gari. Daga Ingila labarin auduga ya tayar wa da kamfanonin sarrafa auduga, wato *Cotton Manufacturing Company* hankali sosai. Don haka sai waxannan kamfanoni suka tara kuxi dala xari shida (600) suka turo wani malamin makaranta mutumin Jamaika, da ya zo

---

[1] C.R. Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na 43 zuwa 44.

[2] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*; shafi na 4 zuwa 5.

yankin Neja ya nemo masu auduga. Sunan wannan mutumi Mista Robert Campbell. Shi Mista Campbell sai ya niqo gari ya taho Abeokuta.

A Amirka kuwa, akwai dubban 'yantattun Bayi waxanda cinikin xan-Adam ya kai su can, akwai kuma mutane masu nema masu 'yancin kai, wato 'yancin da zai maida su dai-dai da farar fatar Amirka. Daga cikin waxannan mutane, akwai wani Baqar Fata xan Gwagwarmayar neman 'yanci mai suna Likita *Martin Robinson Delany*, shi ma ya zo yankin Neja don nema wa 'yan uwansa Baqaqen Fata wurin komowa, saboda an fahimci Baqaqen Fata ba za su tava samun 'yanci ba.

Fahimtar wannan ta sa aka yi ta qoqarin dawo da su qasar haihuwarsu wato Afirka. Burin qungiyar wannan likita shi ne kwaso xaruruwan Baqar Fatar Amirka wato *African-Americans*, daga qasar Kanada da Amirka zuwa Afirka. Rahoton da aka samu na Auduga a Abeokuta ya jawo hankalinsu zuwa wannan gari da ke Yammacin Afirka. Likita Delany ya zo Abeokuta qarqashin qungiyar wayar da kan Afirka wato *African Civilization Society*.

Garin Abeokuta sai ya samu manyan baqi, ranar 5 ga Nuwamban shekarar 1850, Likita *Martin R. Delany* da Mista *Robert Campbell* sun haxu a wannan gari, Mista *Samuel Ajayi Crowther* shi ne ya ba su masauki. Saukar su garin Abeokuta ke da wuya, sai Mista *Campbell* ya shiga tattaunawa da 'yan fataucin auduga, ya tsara su sosai ya kuma jawo hankalinsu.'Yan fataucin sun amince masa, sun kuma ba shi goyon baya tare da tabbatar da cewa Ingila za ta samu auduga isassa. Shi ma Likita Martin ba a bar shi baya ba wajen nema wa Amirka kasuwar auduga. Fataucin auduga da ake yiwo wa daga Arewacin wannan yanki, sai ya tashi haiqan a garin Abeokuta.

Garin Abeokuta ya qayatar da Likita Martin sosai, don haka sai ya tattauna da shugabannin Yarbawa da Alake, wato Sarkin Abeokuta bisa gagarumin abin da ya kawo su da neman yarjejeniya da su bisa neman qasa don kwaso dubban Baqar Fatar Amirka zuwa garin Abeokuta.

Likitan ya yi wa shugabannin Yarbawa bayanin cewa akwai xaruruwan Amirkawa da ke son komowa qasar haihuwarsu Afirka don zaman su a Amirka yana gallabar su sosai. Ya jaddada wa shugabannin cewa, zuwan Amirkawa qasarsu zai kawo masu ci gaba ta fannin qarin ilimi da sana'a da fasaha da bunqasar noma da kuma ma'aikatu.

Jin wannan kalami na Likita Martin, sai shi Alake na Egba-Land tare da jama'arsa suka ba da goyon bayansu, suka kuma amince da za su karvi Amirkawan hannu biyu-biyu. Ranar 27 ga watan Disamban shekarar 1859, sai Alaken tare da 'yan Majalisarsa suka sanya hannun karvar *Afro-Americans* da kuma ba su muhalli a garin Abeokuta. Likita Martin da Mista Robert suka sa hannu a wannan yarjejeniya a matsayin wakilan Baqar Fatar Amirka.

An tashi wannan taro kowa na cike da farin ciki. Shugabannin Yarbawa na murna, Amirkawa za su zo qasarsu, su kawo masu ci gaba. Manyan baqinsu ma

na murna don kowannensu ya samu biyan buqata, amma ba kamar likita wanda yake gode wa Allah tunda ga shi ya samo wa 'yan uwansa qasar da za su komo ba. Likita Martin da ma ba ya son a ci gaba da kai 'yantattun bayi qasar Laberiya saboda ya hangi za ta zama hannun rediyo ga qasar Amirka, don haka yake so a nemi wani sabon wuri a Yammaci na Nahiyar Afirka, to, ga shi ya samo garin Abeokuta. Wajen maganar auduga kuwa, kowannensu na murna domin Ingila da Amirka sun samu kasuwar auduga.

Likita Martin ya samu watanni biyar a garin Abeokuta yana tattaunawa da shugabannin Abeokuta da 'yan fataucin auduga, kafin ya koma gida sai da ya yi 'yan bincike-bincike game da cutuka iri-iri da suke addabar mazauna wannan wuri, ya kuma bayar da shawarwarin yadda za a bi a shawo kan wannan matsala. Manyan baqin sun bar yankin Neja suna cike da farin ciki don kowannen su ya samu abubuwan da ya zo nema.

Komawar Likita Martin Amirka ke da wuya sai ya ba da rahoton tafiyarsa Afirka, ya kuma tashi haiqan wajen ganin wasu rukuni na Amirkawa sun fara tasowa daga Amirka da Kanada zuwa garin Abeokuta. Amma abin takaici sai wannan gagarumin shiri yaci tura, saboda wasu dalilai, idan da haka ba ta faru ba da yanzu akwai zuriyar Amirkawa zaune a Jihar Ogun.

Dalilan da suka kawo rashin nasarar wannan shiri suna da yawa. A lokacin da Likita Martin ke fafutukar kwasar Amirkawa Baqaqen Fata zuwa garin Abeokuta sai yaqin basasa ya varke a qasar Amirka. Wannan ya tilasta wa baqaqen fatar vugewa da shiga aikin soja, shi ma madugun tafiyar sai ya shiga aikin soja. Saboda qwazon Likita Martin shi ne Baqar Fatar farko da ya kai muqamin Manjo a cikin rundunar sojan Amirka wato *Union Army*. A wannan lokaci har ya samu yabo daga shugaban Amirka, Mista Abraham Lincoln. Yaqin basasa ya kawo cikas qwarai da gaske wajen ci gaba da shirin kwaso Amirkawa zuwa gida Afirka.

Shugabannin Yarbawan Abeokuta, ko da yake sun yarda da shirin, amma ya kaucewa al'adarsu, don al'adarsu ba ta yarje wa wani bare ya zo ya mallaki qasa a qasarsu ba. Yaqe-yaqen da qasashen Yarbawa ke fama da su tsakanin su a wannan lokaci bai ba da damar samun sukunin ci gaba da shirin ba. Manyan Mishan waxanda za su faxa a ji, sai rikici ke varkewa tsakaninsu sabili da kasuwancin auduga da suka yi dumu-dumu a ciki, suna babakere tare da handama. Saboda haka babu wani mai faxa a ji a cikinsu ballantana a yi amfani da shi wajen cimma nasara.

Wani dalili babba da ya yi hani da ci gaba da shirin komowar baqar fatar Amirka zuwa garin Abeokuta, shi ne rashin isassun kuxi. Yaqin basasar Amirka shi ya kawo wannan wahalar kuxin.

Ko da yake Likita Martin tare da qungiyarsa sun yi matuqar qoqarin ganin 'yan uwansu sun dawo gida, amma burinsu bai cika ba saboda matsalolin da suka kawo wannan babban shiri yaci tura. To, me ya sa Ingila da Amirka suka qwallafa

ransu wajen neman auduga idanuwa a rufe? Vullowar masana'antu, wato *industrial revolution* tare da samun injunan saqe-saqe sun tilasta su neman kayayyaki fiye da bayi. Yaqin basasar Amirka ya qara tsananta qasashen Amirka da Ingila neman auduga.

Amfanin wannan abu yana da yawa, da ita ake saqe-saqen suturu iri-iri da kayan Sarki, wato soja da 'yan Sanda da sauran ma'aikatan tsaro. Qarin yawan sojoji shi ya qara wa Turawa qaimi wajen neman auduga idanu rufe don a qara yin kayan Sarki na sojoji da 'yan Sanda. Idan mutum ya yi la'akari da cewa a wannan zamani babu hanyoyin yin saqar sutura da suka wuce auduga, to, sai ya fahimci dalilan da suka sa farashinta ya yi ta hauhawa kuma aka yi ta neman ta idanu rufe.

Babban kamfanin da ke saqa da auduga wanda ake kira *Lancashire's Cotton Mills* da ke Ingila ya shiga wani hali na qaqa-ni-kayi a farkon qarni na ashirin. Wannan kamfani wanda shi ne masana'anta mafi girma, kuma yake tashe tun cikin qarshen shekarar 1700, sai ya shiga matsalar qarancin auduga. Kamfanin yana da ma'aikata wajen miliyan uku, kuma yana saqa kayayyaki iri-iri da auduga. A wannan lokaci kayayyakin da ake yi da auduga sun yi yawan kashi xaya bisa uku na duk kayayyakin da Ingila ke sayarwa a qetare, ana kuma samun fam miliyan xari a shekara. Amma a cikin shekarar 1901-1902 sai kamfanin ya shiga matsalar samun auduga.

Tun kafin wannan lokaci kuwa, Turawan Ingila ke ta fafutukar neman auduga saboda bala'in annobar ciwo wato *plaque* ta kashe manoman auduga da yawa a qasar Amirka inda kamfanin ke samun auduga. gwamnatin Amirka ma ta tashi tsaye haiqan wajen sarrafa audugar da take nomawa, saboda haka sai kaxan suke sayar wa Ingila. Waxannan dalilai sun tilasta wa Ingila neman kasuwar auduga. Amma samun auduga a Yammacin Nahiyar Afirka ta qara wa wa nnan yankidaraja qwarai da gaske, saboda haka ne Firayim Ministan Ingila na wannan lokaci, Mista *Winston Churchil* ya kan ce, "zaren da ya haxa Ingila da Yammacin Afirka shi ne auduga. "

Shigar Turawa Arewa sai suka duqufa wajen neman auduga da matakan da za su bi su wawashe ta. Binciken da suka yi a shekarar 1904 ya nuna akwai wurare da yawa a Arewacin Nijeriya wanda qasar wajen ta dace da auduga fiye da kowane wuri a duniya baki xaya, kuma waxannan wuraren za su samar da audugar da za ta ishi kamfanin auduga da ke *Lancashire*.

Kasuwar Auduga

Jan S. Hogendorn, wanda ya yi bincike a kan gyaxa da auduga, cewa ya yi qasar Ingila ta shiga wani mawuyacin hali saboda qaracin auduga. Saboda Masaqar *Lancashire* ita ce ta fi kowace ma'aikata girma a wannan lokaci; tana da ma'aikata miliyan uku a qarqashinta. Tun a qarshen shekarar 1700, tana kuma

samun fiye da fam million xari (£100m) a shekara. Haka kuma kayayyakin masaqun sun yi yawan xaya bisa ukun kayayyakin da ake kaiwa qetare. Don haka ne, auduga take da daraja qwarai da gaske.

Ko da yake Ingila na samun audugu daga qasar Amurka, sai aka yi wata annobar qwari wadda ta lalata auduga har ta yi qaranci; sannan kuma ita ma qasar Amurka neman audugar take wurjajan. Gida bai qoshi ba, ai ba a maganar kai wa waje.

Ana cikin wannan matsanancin hali ne, sai ga shi Ingila ta yi gamo-da-katar; ga lambun auduga a Arewacin Nijeriya. Don haka fa sai idanu suka koma Arewa. A shekarar 1904, Qungiyar Manoman Auduga Ta Ingila, wato *British Cotton Growing Association* wadda aka fi sani da *BCGA*, sai ta nemi a ba ta izini ta baiwa qasashen Arewaci da Kudancin na Nijeriya taimakon kuxi don su himmatu wajen noma auduga. Saboda haka sai aka shiga yarjejeniya da shugabannin waxannan wurare a shekarar 1907.

An cimma matsaya a wannan yarjejeniyar a tsakanin shekarar 1907 zuwa 1910 da za a baiwa *BCGA* fam dubu shida (£6,000) daga dukiyar jama'a, ita ma qungiyar za ta ba da kamar su wajen yin abubuwa kamar haka: (1) aikin bincike wajen samar da irin-auduga daban-daban da samar da taki da inganta shuka, (2) raba iri ga manoma, (3) nemo yanki mafi dacewa da noman auduga, (4) ayyukan mishan da za su sa qauyawa noman auduga.

Saboda darajar auduga da tallafin maqudan kuxaxen da aka tara, suka sa aka bunqasa noman auduga da gina wuraren sarrafa ta da ake kira *BCGA*, a sassa daban-daban a Arewacin Nijeriya. Dalili kuwa shi ne bincike ya nuna Kudancin Nijeriya bai dace da noman auduga ba. Amma kuma, Arewacin Nijeriya shi ya fi dacewa da noman auduga, a faxin duniya baki xaya. Binciken da aka yi a shekarar 1904, ya ba da rahoton cewa: "Masu yi wa qungiya bincike sun ruwaito cewa, akwai isassar qasa mai albarka; wadda ta dace da noman auduga. Akwai kuma ma'aikata. Hasali ma, cikin qasar wasu yankunan ma, an ruwaito cewa su ne suka fi ko ina dacewa da noman auduga a duniya. An kuma qiyasta cewa a wannan yanki kaxai, za a iya noma audugar da za ta ishi masaqar Lancashire qwarai da gaske. " [1]

Domin jin daxin samun wurin noma auduga isasshe, sai kakakin Qungiyar *BCGA* da suka je wajen Firayim Ministan Ingila Mr. Campbel Bannerman, ya ba shi albishir da cewa Masaqar *Lacashire* za ta iya samun "ceto " daga Arewacin Nijeriya, ta kuma "qwaci kanta " daga dogaro da Amurka.[2]

---

[1] Jan S. Hogendron, *Nigerian Groundnut Exports: Origin and Early Development*, Ahmadu Bello University Press Zaria, (1978) shafi na 16 da 17.

[2] *Ibid.*, shafi na 18

A wannan gwagwarmayar neman ceto, sai aka maida Kano da Zariya, manyan cibiyoyi na bunqasawa. Don haka sai babban ma'aikacin qungiya wato *Chief Agent* na *BCGA*, Mista *Percivial* ya taso takanas don ya kawo ziyara ga waxannan garuruwa, Mista *Percivial* da tawagarsa sun gamsu da abubuwan da suka ji suka kuma gani, a wannan muhimmiyar ziyara da suka kai birnin Kano.[1]

Haka kuma shugabannin qasar Ingila sun yi farin ciki da samun wajen ceto mai amfani. An ce ma Xan Majalisa, *MP Winston Churchill* (daga baya ya zama Firayim Minista) ya nuna sha'awarsa a kan abubuwan da aka hango wajen samun auduga. Ita ma uwar gidan gwamnan Arewa, wato *Lady Lugard* sai da ta rubuta a littafinta a shekarar 1905 cewa, "lardin Kano cike yake da auduga, ana noma ta da killace gonakin auduga ."[2] Mista *H.R. Palmer*, Razdan na Kano a shekarar 1908, shi ma ya ba da shaidar cewa Lardin Kano zai zama wajen noma auduga ne da hatsi.[3] Arewa ta zama wata daula ta auduga, ta kuma ceto qasar Ingila a lokacin da ta shiga qaqa-ni-kayi wajen neman audugu.

A cikin watan Disamba na shekarar 1905, aka samu sauyin mulki a Ingila. Xan Majalisa *Winston Churchill*, sai ya zama Sakataren Qasashen Renon Ingila wato *Under-Secretary for the Colonies*, sai ya maye gurbin *Marlborough* wanda shi kuma ya zama Mataimakin Shugaban Qungiyar *BCGA*. Da samun waxannan sauye-sauye, sai maganar aikin jirgin qasa da zai haxa garin Baro da Birnin Kano, ya taso haiqan. Saboda ba yadda za a yi Ingila ta ci arziqin da ke damvare a Arewa ba tare da yin wannan muhimmin aiki ba.

A lokacin da manyan qasashen duniya suke neman auduga ido a rufe, Allah Ya azurta Arewa da ita sosai. A wannan zamani kusan gonar kowa da ita, saboda yawanta ma a kowane gida ka je za ka ga mata na kaxi, suna yin zare da abawa. Mazaje suke saqa tufafi iri-iri kamar su rigar saqi da wandon saqi da barguna da zannuwa da sauransu. Irin rigunan wannan lokaci manya-manya ake yinsu don har kusan jan qasa suke yi idan ana sanye da su, ba domin komai ba sai don yalwar auduga da basirar masu saqar, sannan kuma tare da matukar son rufe tsiraici. Masaqa da Marina sai hidimarsu suke yi, sana'arsu na bunqasa shekaru masu yawa kafin zuwan Turawa qasarsu.

To, me ya tilasta Turawa shigowa Arewa? Idan mutum ya amsa wannan tambaya da cewa ko Turawa su shigo Arewa, ko su tafi tsirara ba za a qaryata shi ba. Don kuwa sun daxe suna Allah-Allah su shigo Arewa, da shigowarsu ba abin da suka yi shirin yi sai aikin shimfixa hanyar jirgi (Daga Baro zuwa Kano) ba abin da suka riqa xiba ido rufe kamar auduga!! Auduga suka fi sani, ita kuma ta fi

---

1 *Ibid*.

2 Jan S. Hogendron, *Nigerian Groundnut Exports: Origin and Early Development*, Ahmadu Bello University Press Zaria, (1978) shafi na 16 da 18.

3 *Ibid*., shafi na 19.

komai daraja a wannan lokaci. Turawa sun shigo Arewa domin kwasar arziqinta baki xaya.

Vullowar Turawa 'yan kasuwa a Arewa, ya sa darajar kayayyakin gona fitowa a hankali, su ma kasuwarsu sai ta fara bunqasa cikin hanzari. A kudancin wannan qasa, kasuwar manja ke tashe wanda ake amfani da shi wajen yin sabulu da sauran su. Binciken da Turawa suka yi a shekarar 1910, ya fito da ximbin kayayyaki masu daraja waxanda suke jibge a Arewa, kuma suna da tsadar gaske a birnin London.

Lardunan Sakkwato da Yola da Barno suna da danqo wato (Gum) mai daraja ta xaya da irin danqon da ake samu a qasashen Sudan da Senegal. Akwai rama (Fibre), mai qarfi da daraja, farashin tan guda fam goma sha-shida zuwa fam goma sha-bakwai. Akwai Alkama mai kyau da daraja a sassa daban-daban a Arewacin wannan qasa, farashin kwata guda a birnin Landan sulai 36s:6d (sulai talatin da shida da sisi). Dawa (Guinea Corn) ta ci kasuwa a London, ana sayar da kwata guda sulai ashirin da uku. Kuxin qoqon qwara kuwa, sulai *arba'in* ne (40s). A kan kowace laba xari uku da tamanin da huxu. Wallahi malam, kanwa (Potash) ce dai yadda ta je Landan haka ta dawo domin ba su gano amfaninta ba! Sauran kayayyakin da suka yi kasuwa su ne Fatu da Gyaxa da Kuza da sauransu. A taqaice dai arziqin Nijeriya a Arewa yake a wannan lokaci, don haka shigowar Turawa Arewa idanu rufe ba zai bayar da mamaki ba!

Wani abin mamaki shi ne, Turawa sun daxe suna hanqoron shigowa Arewa, to, waxanne dalilai ne suka hana su shigowa sai cikin shekarar 1900? Dalilan jikirin shigowar su suna da yawa, amma ana iya taqaita su da cewa, Hikimar Allah ce ta yi wa Daular Usumaniyya shinge. Tsofaffi na faxin cewa mulkin Fulani shekara xari ne kurum zai yi. Yaqoqin jaddada Addini na Mujaddadi Shehu Usumanu Xan Fodiyo, an fara su ne a cikin shekarar 1803. Babu wanda ya yi mamaki da ya ga qarewa mulkin nan bayan shekara xari ta cika. Domin a ranar 15 ga Maris, 1903 sojojin Turawan Ingilishi suka isa birnin Sakkwato daga Kano, waxanda ke shugabantar su kuwa su ne Janar *Kembal* da Kanar *Morland*. Wannan ya dasa aya ga mulkin Daular Usumaniyya. Ya kuma dasa Mulkin Mallaka a Arewa.

Mulkin Mallaka a Arewa

Turawan kantin kamfani ne suka share filin shimfixa Mulkin Mallaka, a qasar Hausa. Sun yi qokarin yin amfani da sojojinsu wajen abin da da suka kira, aikin tsaro da kawo zaman lafiya. Amma sai gwamnatin Ingila ta ga lallai aikin tsaron qasar nan ya fi qarfin Turawan Kamfani. Domin kuwa ba alhakkinsu ba ne, tunda su ba masu mulki ba ne, masu ciniki ne kurum.[1] Saboda wasu dalilai masu yawa,

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na 7

sai gwamnatin Ingila ta ce ta karvi mulkin wannan qasa daga hannun Kantin Kamfani.

A cikin farkon watan Janairun shekarar 1900, Ingila ta kafa hukumomi biyu a Nijeriya. Aka sami Nijeriya ta Arewa, da Nijeriya ta Kudu, a qarqashin jagorancin Gwamna Lugga. An danqa masa mulkin wannan qasa a ranar Litinin 1 ga watan Janairun shekarar 1900, aka kuma yi shela don a sanar da jama'a wannan sabon mulki. A cikin wannan yekuwar an shaidawa jama'a cewa:

> *Dukkan jama'a su sani cewa, da iznin Mai girma Sarauniyar Ingila, wadda ke iko da qasar Ireland, mai mulkin Indiya, sha'anin mulkin Nijeriya ta Arewa, wadda a ke ambatonta da Qasashen Neja, wadda take tana tsakanin qasar da ke cikin mulkin Faranshi daga Yamma, daga Gabas kuma qasar Jamus, daga Kudu kuma qasashen Kudu har da Ikko, daga wannan rana ta fita daga alhakkin Kantin Kamfani. Har yau kuma jama'a su sani, duka alqawuranda Kantin Kamfani suka yi, domin, ko kuma da yawun Sarauniya, da yardar sakatarenta mai kula da qasashen da ke cikin mulkinta, suna nan yadda su ke, za a kuma ci gaba da yin aiki da su, tsakanin Sarauniya, da Sarakuna, da dukkan shugabanni. Irin kuma dukkan alqawuran da aka qulla xin nan tun da, kowannensu zai riqe su, ya yi aiki da su. Kuma duk irin damar yin abubuwa, da sunayen sarautu, da sauransu, ko na mene ne, da suka jivinta da waxannan alqawura, dukansu sun koma hannun Sarauniya ke nan. Kuma duk irin xawainiyar da Kantin Kamfani ke yi da, to, nan gaba duk Sarauniya za ta xauki nauyin yin Haka nan. Har wa yau kuma, jama'a su qara sanin cewa Sarauniya tana murnar sanar da su ta naxa Gwamna domin wannan qasa da ke qarqashinta, Kanar Frederick John Dealtry Lugard (da lambobin girmansa kuwa), shi ta naxa. Cewa shi wannan Frederick Lugard har ma ya yi rantsuwa ta kama wannan aiki na wannan qasa. Darajar wannan ita ta sa ya yi wannan sanarwa, ya sa hannunsa ya kuma buga hatiminsa, ranar nan ta xaya ga watan Janairu, hijira tana da shekara dubu da xari tara dai-dai.*
>
> (Sa hannu) **F.D. Lugard**.[1]
> 1 ga Janairu, 1900

Ko da Gwamna Lugga ya angije Daular Usumaniyya ya kafa Mulkin Mallaka, wanda ya yi qoqarin kawar da zaluncin mulkin kama-karya ya kuma kawo sabon

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na . 10-11

tsarin mulki na zamani, amma sai yanzu ne ake ganin wasu illolin wannan mulki da tasirinsa musamman a kan Arewa. Shi wannan mulki, sai ya kawo rikirkitaccen zamanin da yake rusawa Arewa shika-shikan kafuwarta guda biyu: Makarantun Allo da Mulkin Sarakuna, waxannan su ne illoli mafiya muni da aka yiwa Arewa. Saboda da waxannan qafafuwa biyu ne, wannan qasar ta tsaya dimirmir ta kuma tafi kafaxa da kafaxa da sauran qasashe kafin zuwan Turawa. Sannan kuma tasirin wannan mulki ya canza qoqon zuciyar xan Arewa daga son al'ummarsa zuwa mai matsanancin son kansa, amma kishin al'umma sai nadiri abin da ba a rasa ba. A kuma wannan lokaci, wasu 'yan boko sun yi aikace-aikace da niyyar gyaran al'amura, amma sai suka vata su wataqila a rashin sanin illolin hamayya da Sarakunansu da mummunar tasirin mulki ta kan Sarakuna.

Babban makamin da Turawan Mulki suka yi amfani da shi kuwa wajen cimma muradinsu shi ne ta hanyar yaxa ilimin boko da suka baiwa Musulmin Arewa, da nufin kada ya kai su gaba, amma kuma ya maida su fifa-iya-koma baya. Sun kuma samu cin nasara wajen gina tarbiyya a kan tafarkin aqidojinsu, waxanxa suka kaucewa Addinin Musulmi, ba tare da sun soke wannan Addini ko sun maye gurbinsa da addinin Masihiyya da suka zo da shi ba. Amma waxannan aqidoji da suka kawo sun yi wa koyarwar waxannan addinai na Islama da Masihiyya, karen-tsaye a fakaice. Ya kamata mutum ya fahimci yadda aka rusa tsarin Makarantun Allo da mulkin Sarakuna kafin ya fahimci matsayin Arewa a yanzu. Babu yadda za a maida Arewa kidahuma, sai an rusa ruhinta da gangar jikinta. Makarantar Allo ce ruhin Arewa, Sarakuna kuma shi ne gangar jikinta.

A cikin sabon tsarin Mulkin Mallaka sai aka samu tufka da warwara, a tsakanin koyarwa addini da koyarwarsu. Sheikh Na'ibi Sulaiman Wali, wani mashahurin malamin tarbiyya, ya bayyana wannan al'amari, kamar haka:

> "Suka ce, "kimar xan-Adam duka ta dogara ne da irin abin da zai iya tarawa na samun duniya wato addinin yana cewa Mutum shi ne, sa'an nan abin duniya. " Su kuwa suna cewa "A'a, ai abin duniya shi ne gaba, sa'an nan mutum. " Wato saboda haka a kan wannan falsafa duka al'adun suka baibaye duniyarmu suka ginu.
>
> Wanda duk wannan makarantar ta shige shi sai ya halatta yin komai don ya sami samu! A wajensa ya halatta ya yi sata, ya yi qarya, ya yi zamba, domin kuwa shi ne "wayewa " kuma ya halatta ya yi qwace ya yi fashi ya danne da qarfi don ya fizge, domin kuwa guminsa yake ci, domin da qoqarinsa ya samu! Waxanda kuwa duk suke qyamar wannan koyarwa, suke mamakin ta, to su ne "gidadawa " waxanxa ba su ci gaba ba. "[1]

[1] Na'ibi Wali, *duniya Ina Za Ki Da Mu?* shafi na 7

Babu yadda wannan mugunyar al'ada ta jari-hujja za ta kafu in Makarantun Allo da mulkin Sarakuna na raye, suna kuma tafiya sosai kamar yadda ake so. Saboda haka ne Mulkin Mallaka ya yi amfani da su, na tsawon wani lokaci kafin ya tarwatsa su. Da haka ne, aka samu damar cunkusa wa 'yan bokon Arewa wannan al'ada ta "nafsi-nafsi " (kaina-kaina) domin ta maye gurbin ta "ummati-ummati! " (al'ummata-al'ummata) wadda ta samo asali daga Manzon Allah (SAW) aka kuma qara assasata tun a zamanin Shehu Mujaddadi. Ita wannan muguwar falsafa, ita ce qa'idar koyarwar Turawan mulki ta farko. Qa'idar koyarwarsu ta biyu ita ce:

"Kowa sakakke ne, wato yana cikin 'yancin da zai yi duk abin da ransa yake so! Wannan qa'ida ta sa mutum zai iya yin duk abin da zai yi don qosar da sha'awarsa babu dabaibayi babu linzami. Don haka saduwa tsakanin mace da namiji kowa ce iri ce, shi kuma kowa ne iri ne, muddin dai ransu ya yi masu daxi, to ya halatta! Don haka mutum ya sha dukkan dangin kayayyakin maye da ganye da qwaya muddin dai bai auka wa wani ba, ya halatta, domin kuwa "me ya yi maka zafi? " Wanda ya yi zurfi cikin bin wannan qa'ida zai iya yin yawo tsirara haihuwar uwarsa, kuma yin haka, a wani lokaci, ita ce babbar burgewa. "[1]

To, sai a fahimci waxannan qa'idodi, kafin mu fahimci manufofin Mulkin Mallaka. Ta haka ne, za mu gane dalilan da suka sanya Arewa shiga wani mugun hali a yanzu, da kuma yadda al'amajirai suke cikin wata rayuwa qasqantacciya da kuma rataye mulkin Sarakuna a ragaya da aka yi. Domin kuwa manufar Mulkin Mallaka ta wuce ta kwasar arziqi kawai, ta haxa da sanya tarnaqin hana ci gaba, da yi wa addini karan-tsaye da sauransu. Fahimtar illolin wannan mulki na da amfani sosai, masana kuma sun rubuta littattafai masu yawa a kansa. A lokacin wannan zamani na mulki da kwasar ganimar arziqin qasa, da lalata kyawawan xabi'u, da kafa miyagun xabi'u da sauransu ke aukuwa gaba xaya. Amma kowane abu yana da ajali, idan ya zo ba zai saurara ba, saboda wa'adi ya cika ke nan. Ko da yake Mulkin Ingilishi, ya zo qarshe a shekarar 1960, amma har yanzu gugguvinsa yana nan, da illoli masu hana ci gaba. Domin fahimtar irin wannan mulki ne, sai Sheikh Na'ibi Wali, ya ce:

"Bayan irin wannan koyarwa ta fara zama a kan malaman zaman duniya; sai zalunce-zaluncen xan-Adam ga xan-Adam suka fara yawaita, sai qungiyoyi na qasashen Turai suka ga, bisa fahimtar irin wannan koyarwa, dole ne su mamaye qasashen da duka ba irin nasu ba! Sai suka bazu da wasoso da rububi da haxama, suka mamaye Afirka da Asiya da sauran wurare masu maiqo, masu rauni. Saboda

[1] Na'ibi Wali, *duniya Ina Za Ki Da Mu?* shafi na shafi na 7.

me? Saboda neman samu da gina kai da qosar da kai, ko da waxanda aka mallaka za su tabbata cikin qangi na bauta da talauci da jahilci.

"Sun kawo karatunsu da tsarinsu wanda yake qunshe da ruhin nan na haxama da son kai, sun koyar, ba don a koya a yi dai-dai da su ba, a'a sai don a koya a qara taya su Mulkin Mallaka. Saboda haka aka sami fiye da qarni xaya ko biyu ko uku, suna cikin qasashen mutane, amma mutanen ba su iya komai ba, sai gwargwadon abin da za su iya taimakawa don tafiyar da Mulkin Mallaka. "[1]

Wani babban illar mulkin mulka shi ne na ba da gubar dankwafe al'umma da kuma assasa Mulkin Mallaka. Wannan ilimin boko da aka baiwa Nijeriya ta Arewa yana da matuqar muni, saboda idan ya kafu zai kasafta al'umma zuwa gidaje-gidaje don yin hamayya da juna, a tsari samfurin *Hindu Caste System*. Ana kiran wannan tsarin kasafta al'umma zuwa ajujuwa masu gaba da hamayya da juna "janjani system". Irin wannan tsarin rayuwar al'umma bisa tsarin janjani ne mulkin mallaka ya dasa a Arewa. Shi wannan ilimi da tsarin mulkinsa sun raba xan Arewa da makarantar Allo da mulkin Sarakuna. Tasirin wannan tsari, Jajmananci ne ya taimaka gaya wajen maida Arewa kidahuma a wannan zamani duk da arziqinta na jama'a da ma'adinai. Domin kuwa in ji wannan mashahurin malami:

> *Duk wanda ya raba ka da ta'adunka, da tarihinka, da darajar qasarka, to babu shakka ya yaqe ka fiye da yaqin takobi ko bindiga. Wannan kuma shi ne ake kira Sabon Salon Mullaka.*[2]

Duk wanda ya san tarihin wannan qasa, da bunqasarta a cikin qasashen nahiyar Afrika, ya kuma duba yadda ta tavarvare a duk kusan harkokinta a yanzu, babu shakka zai yarda da cewa Sabon Salon Mulkin Mallaka ya fi illa mai muni tare da mummunan tasiri. Saboda shi ke tafiyar da tsarin Jajmananci sannu a hankali. A wannan zamani an raba jama'a da al'adu da ta'adunsu. Kamar yadda malamin tarbiyya ya bayyana. Al'adu sun game komai da komai, na abubuwan da mutum ya saba yi a rayuwar duniya. *Ta'adu*, kuma su ne kyawawan al'adu da aka tsame don amfanin mutane da gyatta zamansu da mutuntasu.

Alal misali, idan mutum ya aikata wani abu na rashin kirki wanda mutane suka ga bai kyauta ba, su kan ce, "kai wane dai ba shi da ta'adu, amma ba a cewa ba shi da "al'adu, " saboda haka ma iya cewa kowa yana da al'adu, amma ba kowa

---

[1] *Ibid*. shafi na shafi na 8.

[2] Na'ibi Wali, *duniya Ina Za Ki Da Mu?* shafi na shafi na 9

ne yake da ta'adu ba.[1] Saboda haka ma iya cewa, zamanin annabi shaho, da sigar Mulkin Mallaka ya zo ya fauce mana ta'adunmu, sai abin da ba za a rasa ba. Bugu da qari, wannan tsarin rayuwa samfurin Hindu Caste system da Arewa ke bi shine illa mafi muni da mulki ya haddasa mata.

Kowa ne zamani da irin makamin da ake amfani da shi wajen ya qarsa. A shekarun baya, an yi amfani da tsinin mashi ko da qarfin soja wajen cimma manufa. A wannan zamani kuwa, ana amfani ne de ilimin halayyar xan-Adam, da ilimin kimiyya da fasaha, a wajen tabbatar da Sabon Salon Mulkin Mallaka. Makamin wannan zamanin kuwa shi ne dimokaraxiyya. Da wannan salon tsarin mulkin jama'a ne, za a iya kau da ta'adun jama'a, domin a sauya masu da waxanda za su zama tarnaqin hana ci gabansu. Illar Jajmananci mafi muni shi ne bautar 'ya'ya da ya saba domin su dauwama a aji mafi daraja a cikin al'umma. An ce zamani riga, duk qasar da ba ta rungumi wannan tsari ba, an xauketa bagidajiya ce, a harkokin ci gaban duniya a yanzu. Saboda haka kafin mu fahimci yadda wasu 'yan boko, suka yi amfani da guguwar Dimukuraxiyya har suka keta rigar Sarakunan su, sai mu san wace dimokaraxiyyar suke fagauniyar kafawa?

Sheikh Na'ibi Sulaiman Wali, ya yi qulaficin bincike a kan Dimukuraxiyya, wadda ya ce kalma ce da Girkawa na da suka wassafa irin gwamnati ta misali da ya kamata a yi mafarkin samu, don kowa ya ji daxi a cikinta, wato "Aljannar duniya "! Amma irin wannan gwamnati ta mafarki ba za ta samu ba, sai daga baya qasashen Turai suka yarda cewa, "gwamnatin Dimukuraxiyya ita ce tsarin siyasa wanda ta kansa ne jama'a za su zavi mutane masu gudanar da gwamnati a maimakonsu. "[2]

Kusan a ce Dimukuraxiyya ta zama addinin qasashen Turai, kuma qoqari suke yi ta baibaye qasashen duniya baki xaya, saboda su yaxa aqidarsu. Domin haka ne aka gina Dimukuraxiyya a kan abubuwa guda huxu, waxanda su ne shika-shikan wannan aqida, da ake so ta game duniya baki xaya ce. A taqaice dai su ne: Ba Addini (Secularism) – Ba a bin wani addini takamaimai, da Xiyauci (Liberalism, Liberty) – 'Yanci/walwala, da Yanqasartaka (Nationalism) – Kishin qasa, da Mata'i (Materialism) – Tara abin duniya

A kan waxannan gwafofi ne aka kafa Dimukuraxiyya, aka kuma kambama wannan tsarin mulki da cewa, ta wannan hanya ce kawai talaka zai kai ga Aljannar duniya. Domin wannan ita ce: gwamnatin mutane, da mutane suka kafa, saboda mutane, wato da turanci *Government of the People by the People for the People*.[3] Da jin irin wannan kirari da kambamawa, sai hankalin mutanen qasashen

---

1 *Ibid.* shafi na 3

2 Naibi S. Wali, *Dimukuradiyya, WACCE? Islamic Foundation of Nigeria, Kano* (1994) shafi na 3

3 *Ibid.*i, *Dimukuradiyya.*

duniya ya tashi haiqan saboda ganin zuwan wani tsari da zai kai su ga tudun na tsira! Duk tsarin da bai qunshi waxannan shika-shikai ba, mulki ne na zalunci da danniya. Mulki ne kuma mara ba da 'yanci da walwala ga xan-Adam. Ko da yake an fi amfani da xiyauci wato "liberty " ko kuma "Freedom " 'yanci, a wajen tallar sayar da wannan tsarin mulki, yin haka, ya sa mutanen qasashe masu tasowa xaukar gwagwarmayar qwato '"yanci, " wajen neman kafa sabon tsarin mulkin mutane da zai kawar da zalunci a doron qasa.

Da guguwar iskar Dimukuraxiyya ta murtuke a Arewa, sai ga talakawa sun tunzura suna wa Sarakunansu bore, a fagauniyarsu ta neman mutunci da yanci da aljannar duniya. Ashe tarin kumfa su ka yi wa hangen dutse, a lokacin da tekun zalunci ya yi ambaliya ya tumbatsa don ya hallaka jama'a. A cikin wannan ruxu sai suka qi shiga kwamin da Sarakuna ke tuqawa wajen kai jama'arsu ga tudun-na-tsira. Amma masu hikima sun ce, tsuntsun da ya ja ruwa, shi ruwa ka doka! A yau dai, Talaka a Arewa ba shi da galihu har yanzu 'yancinsa yake nema kamar ruwa ajallo, bai kuma samu ba. Wannan illa ce ta Mulkin Mallaka da ke ci har yanzu.

Wani abin da jama'a ba su fahimta ba game da dimukaraxiyya shi ne abubuwan da tsarin mulkin ya qunsa, dafinsu da illolinsu sun fi amfanin da aka ce mutane na samu a qarqashinsa. Alal misali, mata'i wato "materialism " idan ya yi wa jama'a mugun kamu, talaka yake rusawa. Saboda manufar wannan tsarin mulki, shi ne tafiyar da jari hujja ya assasa tasirinsa a kan al'umma. A tsarin mulkin Dimukuraxiyya talakawa ne makamashinsa, saboda xabi'ar naku namu ne, namu na mu ne, wadda ke haifar da ci da ceto. Talaka a wannan tsari ba shi da tasirin komai, duk da cewa yana cikin tsarin mulki ne na mutane wanda mutane suka kafa. Babu wata garavasa da za a samu musamman idan wannan salon mulki na tafiyar da tsarin Jajmananci.

Dimukuraxiyya kamar tattattalin arziqin Turai, wato (Western Economics), talaka take nannagawa, ta kuma qara wa mai qarfi qarfi. Wannan ya sa talaka ke cikin wani mummunan hali a Arewa domin shi ake qonawa don wutar Dimukuraxiyya ta ci gaba da ci balbal. Idan ganin qasqanci ta ishe shi har ya yi ruri saboda matsanancin qunci da azaba, sai a rarrashe shi da cewa, har yanzu Dimukuraxiyya ba ta kai inda ake so ta kai ba, qasar Amirka wadda ke jagorancin Dimukuraxiyya a duniya, har yanzu ba ta kai gaci ba tukun, wato aljannar duniya. Maimakon a tsahirta masa, sai a cunkusa masa *Nationalism* wato kishin qasa ko 'yanqasarta. Saboda wannan tsari ba shi da wata hanyar taimakon talaka, sai alqawarin cewa komai zai masa kyau nan gaba. Dalili kuwa asalinta, mafarki ce, har yanzu da mafarki ake cika manufofinta.

Haka kuma ita Dimukuraxiyya babu ruwanta da addini saboda tana bin aqidar *secularism* ne. Idan haka ne, babu yadda Arewa za ta tafi da tsarin Makarantun Allo waxanxa suke karantar da Alqurani Mai girma bil haqqi da gaskiya. Wannan

ya sa tunda sun qi a gurvata tsarinsu da karatun boko, aka tarwatsa su. A dalilin haka ne almajiran waxannan makarantu ke ganin tasku, da qasqanci da wulaqanci daga 'yan uwansu Musulmi. Abin da ya ci Makarantun Allo, shi ya ci Sarakuna. Saboda su ne wakilan Shehu Mujaddadi. Idan malamai ne fitilun al'umma, to Sarakuna ne direbobinta. Dalilin haka ya sa, aka kifar da su, a fagauniyar kafa mulkin Dimukuraxiyya a Arewa. Duk da cewa ana iya tafiya da su a wannan tsari su kuma bada gudunmawa mai kyau wajen ci gaban al'umma. Talakawan da aka tunzura suka yi wa Sarakuna bore a safiyar mulkin Dimukuraxiyya, su ne abin tausayi a yanzu, saboda su ne karmamin da wutar jari hujja ke qonawa a Arewa, su ne kuma suka zama gasket a Nijeriya a yanzu.

A takaice dai mulkin mullaka ya zo ya sami xan Arewa a matsayin mutum kamilalle mai hankali, zai kuma amsa sunansa mutum, saboda ya kevantu da halaye da za su sa shi amsa wannan suna saboda: "*Mutum shi ne wanda yake da mutunci, wato wanda ya sanya wata manufa tsararriya da yake bi. Wadda a kanta ya yarda ya ba da duk abin da ya mallaka komai tsadarsa; lokaci da dukiya da jini da rai. Manufa wadda saboda ita yake rayuwa ko kuma ya yarda ya mutu.* "[1]

Da waxannan halaye na mutuntaka ne, jama'ar Arewa ta ginu har ta zama abar misali a duniya. Da waxannan halaye ne har Bature ya yi masu jinjina har ya ba su shaidar ficewajen gaskiya da riqon amana, da qwarewa da gogewa wajen adalci a shugabanci, da jaruntaka a wajen yaqi, da juriya wajen sufuri da kasuwanci, da nuna hikima da fasaha wajen aiki tare da ficewajen ilimi da taqawa a wajen malanta. Amma a kusan qarni guda da zuwan Turawa, sai waxannan halaye da suka kafa buwayayyar al'umma da ake kira Arewa suka tasamma narkewa kamar rava da fitowar hantsi. Saboda haka a yanzu kusan a ce babu "yan Arewa " sai dai "mazauna Arewa " domin bambancin ta'adu da manufa. Mazauna Arewa ne kuma suka zamafifa-iya koma baya a Nijeriya. Babu shakka wannan abu ne mai baqantawa mai kuma sanya juyayi, musamman idan aka yi la'akari da cewa wannan kutingwila ta shafi addininmu.

Wannan bayani zai yi amfani wajen fahimtar tasirin mulkin Ingilishi a farkon qarni na ashirin da kuma fahimtar sabon salon Mulkin Mallaka wanda ke cin Arewa a yanzu. A farkon qarnin da Turawa suka shigo wannan qasa sun kafa wasu garuruwa da suka zama hedkwatocin mulkinsu, a lokuta daban-daban. Daga waxannan hedkwatoci ne aka riqa tafiyar da mulkin mallaka a Arewa.

---

[1] Naibi S. Wali, *duniya Ina Za Ki da Mu?* shafi na 9

KASHI NA UKU

Hedkwatocin Arewa

Garin Lakwaja

Ranar Litinin, xaya ga watan Janairu na shekarar 1900, Turawan Mulkin Mallaka *British Crown*, a qarqashin Keftin Lugga suka karvi mulkin Nijeriya ta Arewa daga hannun Turawan kamfani. Shi Keftin Lugga sai ya zama gwamnan farko na sashen Arewa a wannan qasa. A wannan ranar ce kuma ya kwantar da tutar Turawan kamfani, ya tayar da tutar Turawan Mulki da sanyin safiyar wannan ranar a Lakwaja.

Lakwaja ce hedkwatar farko a tsakanin shekarar 1900 zuwa 1902. A wannan gari ne kogin Kwara da kogin Binuwai suka haxe, garin ya daxe da zama cibiyar kasuwancin Turawan kantin kamfani tun a shekarar 1886. Ko da yake an tattauna batun karve usula wato *Charter* daga hannun Turawan Kamfani a *House of Commons* a Ingila a watan Yuli na shekarar 1889, Sakataren Mulki ya bayyana cewa ana iya xaukar garin Lakwaja a matsayin hedkwatar Yankin Arewa, wato *Northern Protectorate* kafin a samu waje mafi dacewa da lafiyar jama'a da ke kuma da hanyoyin sadarwa.

Kafin shekarar 1900 a Lakwaja akwai Zango na Turawan Ingilishi a Arewa da mazaunin Turawan Kamfani wato *Royal Niger Company*. Turawa sun saba da wannan gari, tun kafin su mallaki Nijeriya ta Arewa. An zavi wannan gari ya zama hedkwata saboda yana Arewa, a kan yi zirga-zirga da kwalekwale, da qananan jiragen ruwa a kan kogin Kwara; akwai isasshen ruwa mai kyau wanda yake kwararowa daga tsaunin *Patey*. Amma kuma garin ya cika zafi da yawan duwatsu. Hasali ma dai shigowa cikin Arewa daga wannan gari ba abu ne mai sauqi ba.

Lakwaja ce hedkwatar farko, domin tana da babbar tashar jirgin ruwa, a nan ne kogunan Kwara da na Binuwai suka haxe. Karvar wannan mulki da Turawan Ingila suka yi, sai ya sa Turawa zuwa Nijeriya, domin kasuwanci da tafiyar da Mulkin Mallaka. Saboda wannan dalili ne, sai ya zama tilas a nemi wajen da zai dace da zaman Turawan, wato hedkwata mafi dacewa. Ko da yake kogunan Kwara da na Binuwai suna sauqaqa zirga-zirgar yau da gobe a Lakwaja da kuma garuruwan da suke bakin kogunan, amma abin takaici shi ne, mazauna waxannan wurare na yawan yin najasa a cikinsu.

Wannan abu shi ya sa ruwan kogunan ya gurvace qwarai da gaske har ma ruwan sha ya kan gagara samuwa musamman ma a garin Lakwaja. Duwatsun da suke cikin waxannan kogunan kuma suna yawan lalata jiragen ruwan Turawa,

hasali ma in kogin Kwara ya kawo sosai jirage ba sa yawo. Lakwaja ta cika da karuwai birjik abin qyama.

Hankalin Turawa mazauna Lakwaja ya tashi matuqa gaya saboda irin waxannan matsaloli da suka gallabe su. A cikin rahoton Gwamna Lugga na farkon shekarar 1900-1901, ya ce "Na yi imanin cewa barin wannan hedkwata Lakwaja da kuma matsayinta na mazaunin Turawa, ya zama dole, don haka sai a tashi neman waje mafi dacewa inda najasa ba za ta gurvata ruwan sha ba, kuma duwatsu ba za su lalata jiragen ruwanmu ba. " Turawan mulki sun fi son Kirista fiye da Musulmi, amma saboda tsoron butulci ya sa suke kaffa-kaffa da yaxa addinin Kirista a Arewa. Amma kuma sai suka qirqiro tazarar a tsakanin Musulmi da Kiristan Arewa. Turawan mulki sun baiwa makarantu mishan tallafi sosai amma sun xaqile makarantun gwamnati da suka kafa a garuruwan Musulmi a Arewa. Wannan ya sa Kiristocin Arewa suke kan gaba a wajen ilimin sana'a da kimiyya da fasaha. Ita wannan tazarar itace abar cikewa. Duk da yake akwai babbar tazarar tsakanin 'yan Kudu da 'yan Arewa.

Waxannan dalilai sun qara sa Gwamna Lugga barin Lakwaja Zuwa garin Jebba a shekarar 1902.

Garin Jebba

Da wannan gari Tsangaya ne ga sojojin Yammacin Afirka, wato *West African Frontier Force* (WAFF) a lokacin rikici da Faransa a shekarar 1897 zuwa 1898. Amma garin bai zama hedkwata ba, saboda rahotannin da aka samu a kan garin sun nuna rashin dacewar ya zama hedkwata. Medugbon a kundin bincikensa da ya yi a kan Kaduna ya kawo rahoton *Walter Egerton*, wanda ya yi bayani kamar haka: "Da ma Jebba ba gari ne da ya dace da zama ba. Na ziyarci garin a bara a cikin watan Satumba, amma ban yi mamakin ganin garin cike da sauro ba. Wani baturen kiwon lafiya da ke aiki da relwe, shi ma ya ziyarci garin, ya kuma ba da shawara da Turawa da 'yan qasa da su xauki matakan hana hayayyafar sauro ta hanyar gyaran lambatu da kwatoci, da masai da wuraren da ruwa ke taruwa da makamantansu. Na ga wannan dalilin ne zai hana maida garin hedkwata. "[1]

Duk da haka, maqasudin tashi zuwa garin Jebba shi ne neman wajen da zai fi dacewa wanda zaman mulki da girke sojojin da za a ci Arewa da yaqi. Amma saboda rashin dacewar samun haka, sai aka yi qaura zuwa garin Dungurun a shekarar 1902. Daga garin Dungurun sai aka taso zuwa garin Kaduna kamar yadda za a yi bayani.

Don a cimma wannan buri na samun hedkwata, sai gwamnan ya kafa 'yan qungiyoyin nemo wajen da za a kafa sabuwar hedkwata. Su 'yan qungiyar sai aka

---

[1] Andrew Kayode Medugbon, *Kaduna, Nigeria: The Vicissitudes of a Capital City* (1917-1975), Univeristy of California, Los Angeles Ph.D, (1976), shafi na . 21-22

tura su wurare daban-daban. Manjo Morland, wato Baturen Sojan da ake wa laqabi da Mai-Madubi da qungiyarsa, an umarcesu da su bi tsawon kogin Kaduna. Leftanar *Monk Mason* da ta sa qungiyar su bi tsawon kogin Gurara, shi kuma Leftana *Lowry Cole* da tasa qungiyar su bi tsawon kogin Okwa da ke kan kogin Binuwai.

An umarci dukkansu da su dubo bakin kogunan da sauran wurare, ko sa samo wajen da zai dace da a kafa sabuwar hedkwata. An kuma ba su umarni dukkansu su haxu a garin Girku daga nan su runtuma baki xaya su kawo wa Gwamna rahotonsu. Dukkansu an gargaxe su da kada su yi faxa da jama'a. [1]

Nan da nan sai 'yan qungiyar binciko wajen da za a kafa sabuwar hedkwata suka bazama, kowa ya kama nasa kogin, ya kuma riqi umarnin da aka ba shi. A cikin farkon watan Fabrairu na shekarar 1901, Manjo *Morland*, wanda ya bi kogin Kaduna da Leftanar *Lowry Cole* daga kogin Okwa suka iso Zariya a lokacin, Sarkin Zazzau Kwasau. Su waxannan 'yan bincike sun haxu ne a Girku daga nan sai suka runtuma zuwa Birnin Zariya.

Duk 'yan qungiyoyin binciko inda za a kafa ita wannan sabuwar hedkwata, sun yi kyakkyawan aiki, amma babu wani rahoto wanda ya nuna wani muhimmin waje da zai dace da kafa hedkwatar. Gwamna Lugga har rahoton wajen Jos ya samu, amma bai gamsu ba.

Ganin wannan abu fa sai gwamnan ya ce, ya ga zai fi kyau idan aka matsa gaba kaxan kamar misalin mil ashirin da biyar daga Lakwaja, wato wani gari da ake kira Itobe (Kwandun). Mai yiwuwa garin Kwandun ya dace. Zaven wannan wuri ya zama hedkwata bai yiwu ba, saboda rashin samun wanda zai tallafi wannan aiki don wargajewar ma'aikatar Firdaburdi da kuma qarin bakin Turawa da ake samu daga Ingila, sun tilasta ci gaba da saukarsu a garin Lakwaja.

Hankalin gwamnan yaci gaba da vaci sosai da wannan gari, tunda ban da vataccen ruwanta da duwatsunta, garin sai qazanta da sauro ke qaruwa. Don haka sai bai haqura ba, sai ya ba da umarni da a jarraba garin Jebba, inda a nan ne aka kafa rundunar sojojin Afirka ta Yamma wato (WAFF) amma abin takaici, Jebba da Lakwaja duk shegiyar xarin ce.

Turawa sun tashi tsaye haiqan wajen ganin cewa dai, sai sun sami wurin da za su kafa hedkwata mafi dacewa. Idan Turawa suka sami kyakkyawan muhalli, to, za su ji qarfin tafiyar da Mulkin Mallaka, amma sai ga shi samun wannan waje kusan abin ya faskara. To, wataqila garin Wushishi zai dace don kuwa ana iya bi ta kogin Kaduna a kai gareta. Kuma a kan yi watanni huxu jiragen ruwa na kaiwa da komowa. Waxannan dalilai sun sanya Turawan mulki kwaso kayayyakinsu ta ruwa zuwa ga wannan gari.

---

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na 32.

Kash, zirga-zirgar jiragen ruwa tsakanin Lakwaja zuwa Wushishi akwai haxari qwarai da gaske, saboda 'yan fashi da sun ji motsin jiragen ruwa, sai su yi wuf su fito su wazge dukiyoyin matafiyan. Su waxannan 'yan fashin da ke tsakanin Kwantagora da Bida, sun hana jama'a sakat, saboda yawan fashi. Ganin irin wannan mummunan aikin nasu, sai ya zama ba a qarfafa maganar mayar da garin Wushishi hedkwata ba, muddin dai ba a samu shiryawa da su ba.

Tunda ga shi an rigaya an kwaso kayayyaki masu yawa daga Lakwaja, sai ya tilasta neman wajen da za a zauna, koda a gwaggwafe ne. Wannan ya sa Gwamna Lugga da Likita Langley shugaban likitocin Arewa da Mista *Eaglesome*, Shugaban Firdaburdi da Mista *W. Evan Scott* (Baturen Safiyo) da Keftin *Abadie* (Mai Jimina) suka taso da kansu zuwa garin Wushishi domin su gane wa idanuwansu yadda garin yake. Da kuma hanyoyin da za su bi don su tabbatar da an sami wurin zama. Sun taso a ranar 19 ga watan Janairun 1901. [1]

Da waxannan manyan Turawa suka iso Wushishi, sai Mista *Eaglesome* da Mista *Scott* suka yanki daji suka nufo garin don su duba wajejen da kyau. Daga baya sai suka dawo suka shaida wa Gwamna cewa, a bayan wannan gari za a iya shimfixa hanyar jirgi mai nisan kilomita ashirin da biyar, amma saboda wajen bai cika kyau ba, ruwa zai yi ta varna a kowace shekara, sa'an nan aikin wannan hanya zai xauki tsawon misalin watanni goma sha-biyu.

Jin wannan labari ke da wuya, sai gwamnan ya ce, to, tun da yake wannan sabon wurin da suka dubo bai dace ba, abin da ya fi kyau sai su ci gaba a kan kogin Kaduna, su gani ko sa yi gamo da katar. Da Turawan suka ci gaba, sai suka cimma wani wuri mai ni'ima wanda yake kusan kilomita xaya daga kogin Kaduna, kuma kilomita biyar Arewa da garin Wushishi. Shi wannan wuri da suka samo sunansa shi ne "Zungeru " ko "Dungurun. "

Garin Dungurun

An kafa Dungurun a matsayin hedkwata cikin gaggawa a shekarar 1902. A lokacin da ake neman waje a Arewa da zai dace da zaman turawa da girke sojoji ba tare da mishkila ba. A lokacin ne aka ga dacewar Dungurun saboda ana iya kaiwa ga wannan gari ta kogin Kwara daga Kudu. Sannan garin na gavar kogin Kaduna. Shi wannan kogi ya ratso cikin Arewa daga inda ya ta so daga tsaunukan Filato, yana da tsawon mil 380 ya kuma haxe da kogin Kwara. Saboda haka wannan kogi ya kan xauki jiragen ruwa har na tsawon watanni shida a shekara. Babu sunan waje Dungurun tun fil azal, amma kamar yadda Xantsoho Mohammed ya bayyan a littafinsa *Zungeru. "The Forgotten Capital of Northern*

[1] Abdulmaliki Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na 40.

Nigeria, " kalmar 'Zungeru' ta samo asali ne daga Turawa saboda ba su iya faxin Dungurun sai suka kira wajen Zungeru. [1]

Amma kafin vullowar Turawa da lokacin mulkin Fulani babu wannan gari, marubucin ya yi nuni da cewa wannan wuri ya samo asali ne daga wani mutimi Gbagyi mai kixan garaya wanda ya baro iyalansa ya zauna a gavar kogin Nnamayi. Saboda rashin jituwa da ta auku a tsakaninsu. Daga nan ne sai aka riqa kiran wannan mutum Nda Dungurgi. Wannan kalma 'Dungurgi' kalma ce da ke nuna makaxin garaya da ake kira 'Dungurun'. A wannan sabon wuri sai Nda Dungurgi ya yi suna wajen kaxa garayarsa Dungurun. Daga nan ne sai wannan sabon wuri aka yi wa laqabi da Dungurun. To, a kwana a tashi sai wajen ya zama gari wanda har ya bunqasa ya zama hedkwatar Arewa a zamanin Turawa.

Kamar yadda Nda Dungurki ya ga fa'idar zama a wannan gavar kogi haka suma Turawa suka gani. Amma kafin zuwansu wannan waje sun zauna a Lakwaja. Daga bisani suka bar ta zuwa garin Jabba saboda rashin dacewarta. Amma a shekarar 1900 sai Lugga ya ga ita Jabba kamar Lakwaja take ba ta dace ba. Garin Dungurun sai ya zama mafi dacewa ga dukkansu. Da aka kafa hedkwata a wannan gari sai qauyen Gwarjiko ya sami muhimmanci. A nan ne aka fara kafa hanyar jirgi a Nijeriya. Ita wannan hanyar jirgi mai nisan mil talatin da biyar daga Dungurun ta na da muhimmaci ga Turawan mulki sosai.[2] Garin ya zama hedkwatar Turawan kamfani a shekarun 1890 zuwa 1900.

A kan kai ga garin Dungurun ta kogin Kaduna wanda ke iya xaukar manyan jiragen ruwa wato (Steamers) in ya kawo har na tsawon watanni huxu. Ana kuma zirga-zirga da kwalekwale a kowane lokaci. Wannan kogi mai amfani ya kai har ga Gwarjiko. To, idan za a kai kayayyaki daga qetare zuwa ga wannan hedkwata ko kuma a fita da su, sai a bi da su ta kogin Kaduna har ya zuwa Gwarjiko. Daga nan sai a bi da su ta hanyar jirgi zuwa ga Dungurun. Ka ga ke nan Gwarjiko ta taimaka gaya wajen shige da fice a wannan hedkwata.

Duk da qin garuruwan da ke kusa da koguna da Gwamna Lugga yake yi, wannan sabon wuri da aka samu, wato Dungurun ya qayatar da shi fiye da sauran wuraren da aka dubo. Wannan waje yana da qoramu masu ni'ima, idan kuma kogin Kaduna ya kawo, yana xaukar jiragen ruwa har nisan misalin kilomita goma. gwamnan ya zavi Dungurun da ta zama sabuwar hedkwatar lardunan Nijeriya ta Arewa a cikin watan Fabrairu na shekarar 1901.

Samun hedkwatar ke da wuya, sai nan da nan Baturen safiyo Mista *W. Scott Evans* da Mista *Eaglesome* suka tashi aiki haiqan, jim kaxan har an gina wa Gwamna gida da xakunan ma'aikata ashirin da asibiti da kuma ofisoshin ma'aikata. Kafin watan Maris, al'amarin ginin hedkwata ya yi nisa. Domin rage

---

[1] Dantsoho Mohammed, *Zungeru: The Forgotten Capital of Northern Nigeria*

[2] *Ibid* shafi na 19

wahalar jigilar kwaso kayayyaki zuwa hedkwatar, sai aka shimfixa hanyar jirgi da ta haxe Wushishi (Gwarijuko) da Dungurun. Jirgi ya fara bin wannan hanyar a qarshen shekarar 1901. Turawan mulki sun tare a Dungurun a cikin watan Satumba na shekarar 1902.

Tunda an sami Hedkwatar da ta dace sai aka fara shimfixa Mulkin Mallaka a wannan gari. Wani mulki da ya haifar da illoli masu yawa ba a Nijeriya ta Arewa ba, har da sauran qasashen da Turawa suka mallaka da tsinin mashi.

Mulki Ta Kan Sarakuna

Garin Dungurun ne hedkwatar Arewa daga shekarar 1902 zuwa shekarar 1916. Tana da tsarin mulki da ya dace da mulkn mallaka na wannan zamani. Daga wannan gari ne aka yi mulkin Arewa. A nan ne tushen mulkin gwamnan Arewa wato *Governor of Northern Nigeria* yake shugabanci.

A cikin wannan tsari gwamnan Arewa shi ne shugaban qasa mai cikakken iko. Yana da mataimaka da kuma manyan ofisoshi wato *Principal Officers*, masu taya shi tafiyar da mulkin wannan babbar qasa mai arziqin jama'a da na ma'adinai. Waxannan shugabanni sun haxa da: babban Sakataren gwamnati wato *Chief Secretary to Government* da Babban Mai shari'a wato *Chief Justice* da Atoni Janar wato *Attorney General* da Kwamandan Soji wato *Commandant* da Ma'aji wato *Treasurer* da Daraktan Ayyuka wato *Director of Public Works* da Babban Likita wato *Principal Medical Officer* da Babban Jami'i Mai Kula da Sufuri wato *Chief Transport Officer* da Shugaban 'yan Sanda wato *Inspector General of Police*. Waxannan manyan shugabanni su ne ke taimaka wa gwamnan Arewa a matsayinsu na 'yan Majalisar Qoli Arewa, wato *Executive Council of Northern Nigeria*.

Daga Dungurun ake shugabancin kowane lardi na Arewa takan Razdan xin wannan Lardi. Kowane Razdan yana matsayin shugaba mai cikakken iko wato *Chief Executive*. Wannan matsayi ko muqamin Razdan kuwa na ofisoshin ne, kuma Turawan mulki ne ke riqe da su. Waxannan shugabanni masu zartar da hukunci suna da mataimaka. Domin kowane lardi an raba shi yanki-yanki wato *Divisions*. Kowane yanki yana qarqarshin mulkin mataimakin Razdan ne ko Di'o wato *Divisional Officers*. Haka kuma kowane yanki ko gunduma yana da mataimakin Di'o wato *Assistant Divisional Officers* (ADOS). Ta haka ne gwamnan Arewa ya zartar da mulki Arewacin Nijeriya.[1]

Hanyar tafiyar da Mulkin Mallaka ya bambanta da na kudancin wannan qasa wadda aka mulketa kai tsaye. Nijeriya ta Arewa kuwa sai aka yi mulkinta a fakaice, takan Sarakuna da aka tarar suna mulkin jama'a. Ko da yake Turawa sun sauke waxansu Sarakuna da suka tarar a kan karagar mulki, amma ba su kaucewa

[1] Dantsoho Mohammed, *Zungeru: The Forgotten Capital of Northern Nigeria* shafi na 19

tsarin gadon sarautar ba wajen aiwatar da wannan samfurin mulkin da aka fi sani da *Indirect Rule* wanda shi ma ya haifar da matsaloli masu yawa a Arewa.

Indirect Rule wato mulkin jama'a ta amfani da Sarakunansu. Lugga ya fara kawo wannan batu, sai muqarrabansa *Charles Orr* da *Temple* suka kururuta shi. Gwamna Lugga ne ya aiwatar da shi a Arewa. Da daga bisani Turawan Mulkin Mallaka masana tarihi musamman *Perham* da *Heussler*, cewa suka yi mulkin jama'a a fakaice, a masarautun Arewacin Nijeriya, abu ne da ya wajaba saboda rashin jami'ai da kayan aiki. Domin goyon bayan wannan batu, an samar da wata qididdiga akan girman qasa (faxin mil 320,000 a 1900) da yadda za a karkasa jami'an siyasa ga yawan jama'a sha xaya, ko kuma jam'in mulkin guda xaya ga mutane tsakanin miliyan xaya da miliyan biyu a 1900. Hakan na nuna cewa inda akan akasi aka samu, da Birtaniya ta zavi mulki a fakaice (Mulki a kaikaice ta amfani da Sarakuna) yayin da za a iya cewa dole ta sanya aka yi amfani da wannan tsari, sai dai dalilan da ke nan sun fi na batun fa mutane ko kuxi, saboda babu gaskiya a xauka cewa Birtaniya tana da jami'ai da kayan aiki na gudanar da gwamnati, mulkin Arewacin Nijeriya kai tsaye kuma a lokaci guda, a ce ga Mai girma Sarauniya a sauran sassan Afirka da a Asiya, da *Carribbean*, da Gabas ta tsakiya, da kudancin *Pacific* duk a ji ta a lokaci guda.

Farfesa Alhaji Mahmud Yakubu ya bayyana dalilan da suka tilasta amfani da *Indirect Rule*, a inda ya ce:

"Dalilai biyu suka tilasta amfani da wannan tsarin mulki na amfani da Sarakuna wajen mulkin jama'a. Gazawar da Lugga ya yi ya xore da samun biyayya ta al'ummar da Musulmi suka fi yawa ta amfani da qarfi da yaji saboda haka dole a sasanta ta yadda aka xore da cibiyoyin daular musulunci. Bugu da qari, sun tarar akwai qwaqqwarin tsarin mai qwaqqwarar gwamnati, da Birtaniya za ta yi amfani da shi wajen mulkar jama'a, amma ba soke ko maye gurbin wannan tsari ba. Wannan ya haxa da haxe kan waxannan cibiyoyin sarauta waje guda: da amfani da harshen (Hausa) a matsayin harshen qasa da amfani da (Larabci/Ajami) a matsayin harshen mulki waxanda dukkansu aka tsara hanyoyin rubuta su; aka kuma shigar da su tsarin sharia da kuxaxe. Saboda haka wannan tsarin mulki ba wani koqari ne na Lugga Sarkin qwazo ba kamar yadda wani marubucin tarihinsa ya faxi. Shi Lugga abin daya yi shi ne amfani da wannan dama.

"Ginshiqin mulkin ta amfani da Sarakuna a Arewacin Nijeriya na nan an fa bayyana a Risala ta Wazirin Sokoto, Buhari, da kuma a amsar da Lugga ya bayanni a kai, a jawabin da ya yi a wajen naxa Attahiru na biyu a 1903. Ko da yake Risalar ba da haquri ce saboda miqa kai (yarjejeniya) da Buhari ya cimma da Birtaniya, kamar sauran yarjeniyoyi na kasuwanci ko cinikayya da aka cimmawa da 'yan kasuwa da matafiyana Birtaniya tsakanin shekarar 1823 da

1853, wanda a wannan lokaci da sharaxin Birtaniya ba za ta yi katsalandan da yadda jama'a ke tafiyar da mulkinsu ba, haka nan babu ruwanta da tsarin musulunci wanda a kansa ne aka gina wancan tsarin mulki. Lugga ya yarda da wannan buqata sai dai ya qara da cewa daga yanzu Sarakuna za su dinga gudanar da iko ne a madadin gwamnatin Ingila. Bugu da qari, a wasiqun naxi da ya aikawa Sarakuna, ya tsara ikon da suke da shi da iyakarsu a qarqashin wannan sabon tsari. " Misali, iko akan fili (raba shi ko sayar da shi) duk ya koma hannun gwamnan Birtaniya, haka nan ikon sanya haraji da karvar harajin da yin Dokoki da gyaransu ko soke su duk sun koma hannun Ingila. A gudanar da waxannan iko, gwamnatin Mulkin Mallaka ta xauki xawainiyar tuntuvar Sarakuna da girma tsari da qa'idojin sarauta.

"Duk da haka, akwai babbar matsala a tsakanin masu mulkin na Birtaniya a game da takamemiyar hanyar da wannan mulki zai yi aiki, sannan a tsakanin Sarakuna akwai zargi da kuma xari-xari sun yaxu ko'ina a game da alqawarin da Turawan suka yi na xaukaka tsarin masarautu, cewa hanya ce ta xora mulkin kafirci. Da Turawan Ingilan suka ga hulxa da yawancin Sarakunan tana zama masu matsala, sun yi shirin maido da ainihin Sarakunan qasar Hausa da jihadin da aka yi a qarni na baya ya fara daga sarautunsu.

"Shekaru shida da Lugga ya yi baya Arewacin Nijeriya (a lokacin yana gwamnan qasar Hong Kong tsakanin shekarar 1906 da 1912) ta zama babbar matsala ga muqarraban Lugga wato Temple da Palmer, wajen fayyace dangantakar iko tsakanin gwamnatin Mulkin Mallaka da Sarakuna. Hakan ya qara qamari saboda 'yan xaixaikun Sarakunan da ke son ba da hadin kai, a qarshe sun rasa ta yi domin kuwa sun tarar babu la'ada babu lada sun yi vatan vakatantan. A shekarar 1908, Sarkin Kano, Muhammadu Abbas (1903 – 1919), ya koka a cikin wannan wasiqa da ya rubutawa Rasdan Hewby:

"Ina mai sanar da kai cewa a halin yanzu haka ba ni da aikin yi, saboda haka nake son ka ba ni wasu ayyuka da suka dace in yi. A da ni ba komai ba ne kafin Bature ya mayar da ni Sarki – a yanzu na zama hoto ina zaune ba na yin komai, a kowanne lokaci na kan ji ba ni da lafiya… Kuma tunda kai ne babban Bature, na amince haka za ka ba ni wasu ayyukan yi qwarara da zai farantawa gwamnati rai. Na rigaya na naxe hannun rigata ina jiran in soma aikin da za ka ba ni."[1]

Haka zalika, manyan jami'an Birtaniya na ta matsa wa Gwamna lamba a game da ainihin matsayin Sarakuna. Amma a lokacin da Rasdan na lardin Yola Barclay ya nemi qarin haske a watan Fabrairu na shekarar 1909, ya samu amsa ba tare da vata wani lokaci ba sai dai a harshen sirri da ya yi kama da zaurance;

---

[1] A.M. Yakubu, *An Aristocracy in Political Crisis,* Avery Ashgate Publishing Com. Ltd. England, (1996), shafi na . 24-25

Idan Lugga ya samu Sarki a nasa muqarrabansa labarin daban yake. Ga Temple har ma ga Palmer, gudanar da mulki qarqashin ikon Birtaniya abu ne mai wuyar gaske, sai da aka baiwa Sarakunan babban ikon cin gashin kai. A matsayinsa na Rasdan mai kula da masarautar Katsina a 1907, Palmer ya yi wata Baitul-mali domin adana kuxaxe da aka tara daga harajin da aka karva daga jama'a. A wannan shekarar, En'e ta Katsina ta tara fam dubu bakwai (£7000) inda a ciki Sarki Muhammadu Dikko (1907 – 1944) ya tsara kashe fam dubu huxu(£4000) domin kyautata jin daxin jama'a, sauran fam dubu uku (£3000) ya kashe su yadda ya ga dama. Aka kuma amince masa. Daga bisani a wannan shekarar, Temple ya ba da irin wannan shawarwari ga Kano inda Percy Girouard, Babban jakada kuma Gwamna daga 1907 zuwa 1912, yavullo da wannan shawarwari a sauran masarautu. Waxannan sauye-sauye sun yi sanadiyyar babbar rashin jituwa, har ma da rikici, tsakanin waxannan jami'ai (Temple da Palmer) da Lugga a lokacin da ya dawo Arewa daga Hong Kong a shekarar 1912. [1]

Wannan samfurin mulki, ya taimaka gaya wajen zaizayewar masarauta da tasirinta a hankali. Tsoron da Lugga yake ji shi ne ya zama Sarakuna ke da iko da kuxaxen En'e, zai sa masarautun su zama jihohi masu cin gashin kansu a maimakon vangarori na gwamnati guda xaya. Wannan kamar yadda wani masanin tarihi *Kirk–Greene* ya lura da cewa babu mamaki shi Lugga ya hango, ya sanya ya cire dukkan wani abu da zai ambaci ikon Sarakuna akan kuxaxen shiga na cikin gida a umarninsa na farko ga jami'an siyasa a shekarar (1906) wanda ya zama wani babban sashe na kundin umarnin da aka yi wa gyaran fuska a shekarar 1918. Ga jami'an da ba su da ainihin tabbacin matsayin Sarakuna, Lugga ya jaddada cewa kar a xauka haxa gwiwa ta Birtaniya da masarautu, dole yana nufin wata manufa daban ba. Ya jaddada cewa Arewacin Nijeriya, qasa ce da ke qarqashin riqon amanar Ingila, da Ingilan ke yi wa mulki. Su Sarakuna wakilansu ne kawai. Babu Gwamnatoci guda biyu ta Birtaniya da ta Gargajiya da kowanne ke mulki daban ko sun haxu suna mulki tare. Lugga ya tsara batun kamar haka:

Amma gwamnati guda xaya wacce Sarakunan gargajiyake da kyakkyawan tsarin ayyuka da aka fayyace da kuma matsayi iri guda da aka amince, da jami'an Ingila. Kar ayyukansu su ci karo da juna, kuma ayyukan za su xan zova na juna amma ta xan kaxan, su zama masu tallafa wa juna, sannan shi kansa Sarkin dole ya fahimci cewa

[1] Alhaji Mahmood Yakubu, *An Aristocracy in Political Crisis*, shafi na . 24-25

ba shi da iko da waje ko mulkinsa sai fa ya yi aiki kamar yadda ya kamata ga jiha.

Sai dai gaskiyar da ke cikin failoli na sirri da ke kai komo a cikin sakatariya da ke jagora ga jami'an mulki da ke bakin aiki, shi ne amincewar babu wata nasara da za a cimmawa in ba da goyon baya daga Sarakuna ba. Har ila yau akwai alamun fargaba a tsakanin manyan jami'an Birtaniya cewa a batun biyayyar Sarakuna har lokacin akwai sauran rina a kaba. An tsara tsare-tsare guda biyu domin lallashi da jawo hankalinsu. Na farko shi ne ba da ladar haxin kai ta hanyar ba su albashi mai tsoka daga kuxaxen da ake tarawa na haraji na cikin gida wanda da shi ne za a qarfafa masu gwiwa, kamar yadda suka yi a da domin xaukaka matsayinsu. Jadawali na gaba na nuna albashin Sarakuna da aka zavo, da ake biyansu a kowacce shekara a 1913, ban da alawus-alawus xinsu. Da ke nuna cewa wasu Sarakuna su goma sha-xaya na da albashi fam dubu ashirin da uku da xari biyar da casa'in (£23,590) in an haxa su wuri guda, wanda ba qaramin kuxi ba ne a lokaci guda.

Xaya tsarin shi ne ikon da suke da shi na wanda zai gaji Sarki. A shekarar 1916 aka samar da wani jerin sunayen Sarakuna da waxanda ake jin za su gaje su a masarautu guda talatin da biyar da qananan masarautu. Ko da yake a kowanne babu sunan wanda aka bayar a matsayin mai gado da ya fito ba daga gidan sarautar ba, duk da haka tsarin ya nuna fargabar da gwamnatin Mulkin Mallaka ke da shi na xorewa da kyakkyawar niyyar ta Sarakuna da musamman, xaukar shawarwari gadon.

Ga abin da aka zavo daga wancan tsarin a jadawali na xaya da qe qasa.

Sarakunan da aka zavo da albashinsu a, 1913.

Sarki	-	**Albashi (a fam)**
Shehun – Barno	-	4,800
Sarkin Kano	-	4,800
Sarkin Katsina	-	3000
Sarkin Bauchi	-	2000
Etsun Nupe	-	2000
Sarkin Gwandu	-	2000
Sarkin Zazzau	-	1000
Lamixon Adamawa	-	1000
Sarkin Katagum	-	840

Sarkin Gombe	-	600
Sarkin Argungu	-	550[1]

A shekaru da suka biyo baya, an qara musu albashin ta yadda a shekarar 1935, Sarkin Kano na da albashi fam dubu shida (£6000) a shekara, da alawus na mulki fam dubu biyu da xari biyar (£2,500), da ke nuna ya fi gwamnan Mulkin Mallaka shi kansa. Irin wannan lallashi na qarin albashi da alawus sai ya zama tarko a gaba wanda ya tunzura 'yan siyasa, suna masu yin qazafi da cewa rashawa da tafka maguxi da almubazzaranci sun yi katutu a En'e-En'e waxanda su ne tushen mulkin Sarakuna. Abin lura shi ne don yanzu ra'ayin Sarakuna su amince da mulkin *Indirect Rule* ya sa Turawa ba su qarin albashin da ba su ne suka nema ba. Qarin albashi da alawus ya so ya kawo rashin jituwa a tsakanin Sarakuna, wata mummunar illa da wannan tsarin mulki ya haifar a Arewa. Wannan tsarin mulki ne ya haddasa gaba da, hamayya a tsakanin Sarakuna da 'yan Siyasa ba domin komai ba sai don neman su samu xan qarin albashi. A hankali sai Turawa suka cunkusa wa jama'a son-kai ba son jama'a ba. Saboda ba son jama'a ne ya kawo su ba.

gwamnatin Turawan Mulkin Mallaka ta fahimta sosai da sosai cewa basa iya maye gurbin masarautu na gargajiya, sannan su Sarakuna a nasu vangaren, sai da suka tsaya suka sasanta kansu da qarfin mulki daga waje. Wato sai da aka tsara yadda za a haxa qarfi wuri guda. Tare da tabbacin za a kare martaba da ikon su kansu Sarakunan. Tsarin wannan mulki sai ya maida na kan doki ya koma kuturi. A wannan shiri sai aka yi amfani da albashi domin a samu biyayya da haxin kai. Daga wannan lokaci ne kishin al'umma ya fara zaizayewa masu mulki suka riqa neman qarin albashi don biyan buqatarsu amma ba ta jama'a ba.

Saboda tsarin mulki ne na shugabancin Arewa ta kan Sarakunansu ake kira tsarin da *Indirect Rule*. Wannan tsarin mulki ya baiwa Sarakuna damar tafiyar da mulkinsu kafaxa da kafaxa da Mulkin Mallaka. Amma kowane Sarki yana qarqashin Razdan ne wanda kuma yake qarqashin ikon gwamnan Arewa. Amma da qarshen mulki ya qarato sai Turawa suka riqa zai zaye. Ikon Sarakuna domin mulkin siyasa ya yi tasiri a Arewa. A garin Dungurun aka riqe tafiyar da wannan tsamin mulki kafin a tare Kaduna.

Bunqasar Dungurun

A lokacin da Dungurun ke matsayin hedkwatar Arewa, ta bunqasa sosai, tana da faxin murabba'in mil 2,974 wato "2,974 *square miles* " da kuma yawan jama'a da ya zarce dubu talatin da biyar (35,000). A wannan gari ne Sarakunan Arewa da manyan ma'aikatan gwamnatin mulki da Askarawa ke kaiwa da komowa domin

[1] NAK/SPP10/1/795P/1913: *Sarakuna da albashinsu* (1913)

tabbatar da xorewar mulki na wannan faxexiyar qasar mai kuma ximbin albarkatun gona da ma'adinai. Haka kuma a wannan hedkwatar ce Gwamna Lugga ya kafa Nijeriya a shekarar 1914 wato *Amalgamation of Northern and Southern Protectorate*. A garin Dungurun ne *Indirect Rule* ya fara aiki sosai, don haka ne sai wannan qaramin gari ya riqa cika da jama'a. Sarakunan Arewa kuma suka riqa karakaina tsakanin wannan gari da qasashen su. Sai nan da nan xan qaramin garin ya bunqasa.

Kafa hedkwata a Dungurun ya bunqasa wannan gari cikin xan qaramin lokaci, gine-gine sai qaruwa suke yi domin kuwa sojoji da 'yan Sanda da kuma ma'aikata na qaruwa a kullum. Leburori 'yan safara da fatake da 'yan Janhol sai hallara suke ta yi a wannan gari. Kafin ka ce kwabo garin ya cika maqil da jama'a da Turawa da qabilu iri-iri daban-daban.

A wannan gari ne aka haifi Dr. Nnamdi Azikiwe wanda ya zama xan qasa na farko da ya riqe muqamin Gwamna Janar na Nijeriya. A lokacin da aka haifi wannan mashahurin mutum, a daidai wannan lokaci ne Sarkin Kwantagora Ibrahim Nagwamatse wanda ya yi suna wajen faxa da Nasara ya kwanta dama. A dalilin haka ne sai jama'a suka yi wa Nnamdi laqabi da suna Ibrahim, da nufin shi ma zai taso ya yaqi turawan Mulki kamar yadda Ibrahim Nagwamatse ya yiwa Gwamna Lugga. Ya ko amsa wannan suna domin ya taka rawar gani wajen yaqin qwatowa Nijeriya yanci.

A kuma wannan gari ne aka haifi Ikemba na Nnewi, Cif Odumegwu ojukwu wanda ya shahara a wannan qasa. A garin Dungurun ne kuma wani qasaitaccen mutumin Austria, wanda kuma ya kafa Qungiyar 'Yan Sikawut wato Sir Henry James Speed ya rasu, kabarinsa na nan a wannan hedkwatar Nijeriya ta Arewa. A lokacin da Dungurun ke tashenta akwai xaruruwan mutanen qetare Turawa da Bakar Fata a cikinta. Akwai kuma kaburukansu da yawa a wannan gari wanda ya taso da qarfin iko da bunqasa cikin hanzari.

Tunda Turawan mulki sun sami hedkwata, kuma sun ci qasashen Hausa masu yawa da yaqi, sai shirye-shiryen yadda za a tafiyar da Mulkin Mallaka suke yi. Su waxannan Turawa da masun zaqu da su shigo qasashen Hausa don su kwashi ganimar arziqin da Allah Ya albarkaci wannan vangaren duniyar. Kwasar garavasa ne ya fito da su, don haka sai suka shiga xaura niyyar da kuma qulle-qullen dabarun da za su bi don cimma burinsu.

Shirinsu na farko, shi ne jawo leburori na kusa da na nesa, waxanda za a yi amfani da su wajen ayyuka masu yawa. Turawan mulki sun aika wa Sarakunan Hausa da su aiko da mazaje nagartattu domin su zo wannan hedkwata don su tallafi muhimman ayyuka da za su kawo bunqasar qasashensu. Sarakunan kuma

sun yi na'am da wannan batu, lokaci kaxan sai ga Dungurun maqil da jama'a ta rikixe babban gari.

Su waxannan jama'a da suka hallara a wannan hedkwata, kuma suka zo daga garuruwa daban-daban, su ne ake yi wa laqabi da Dungurawa. Dungurawa, qabilu ne daban-daban da suke zaune a wannan hedkwata, wato Dungurun.

Mafi yawan Dungurawan Hausawa ne, daga nan sai Nufawa da sauran tsirarun Yarbawa da Ibo. Su waxannan qabilu sai suka naxa Sarakunansu, don samun jin daxin tafiyar da sha'anin yau da gobe. Malam Babale shi aka naxa Sarkin Hausawa. Wajen limancin sallah, wani malami mai suna Malam Jafaru shi ke yi wa Musulmin Dungurun limanci. Shi wannan malami shi ne kuma aka zava domin ya zama magatakardar Gwamna. Malam Jafaru, wato limamin Musulmi ne, kuma magatakardar Gwamna. Ban da limanci, aikin wannan malami shi ne ke rubuta wa Gwamna wasiqa ko karanta ma sa wasiqa a cikin Larabci ko Ajami. Duk lokacin da aka buqaci rubuta wasiqa zuwa Sarakunan Hausa, aikin Malam Jafaru ne ya rubuta, in kuma sun rubuto wa Gwamna, ya karanta masa.

Wajen kasuwanci kuma, Malam Muhammadu aka bai wa sarautar fawa. Aikinsa shi ne kwangilar kai nama ga sojoji da 'yan Sanda da asibiti da sauran ma'aikata. Malam Aminu Ilori shi ne xan kwangilar aikace-aikacen gidaje.

Wajen shugaban leburori wato Alaro kuwa, dole ne a samu mutum nagartaccewanda zai shugabanci waxannan dubban leburori, kuma qabilu iri-iri. Turawa suna daraja wannan shugabanci wato (Labour Leader), domin in ba a sami shugaban qwarai ba, to, ayyuka da dama ba za su yiwu ba. Shugabancin leburori, muqami ne mai daraja ga Turawa. Don gudun kada su yi zaven tumun-dare, wajen wannan zave na shugaban leburori, sai Turawa suka sanya cewa a yi jarabawar cin wannan muqamin na shugabancin leburori ko sarautar Alaro.

Naxin Sarkin Alaro

Domin neman wannan sarauta ta Alaro wato leburori da kuma shugabancin leburori, an ce Turawa sun sa jarabawa. Sun tanadi kayayyaki iri-iri a cikin wani xaki, sa'an nan suka rufe xakin. Sai aka tara jama'ar da ke neman wannan sarauta ta Alaron aka ce da kowane ya shiga wannan xakin (mai kayayyaki iri-iri), ya fito ya yi wa Turawa bayanin abin da ya gani a cikin wannan xakin.

Kowane mutum in ya shiga, sai ya fito ya ce da Turawa ya ga kaza da kaza, wato sai ya lissafta abubuwan da ya gani a wannan xaki, sai Turawa su ce masa ya tafi ya ba su waje ai su ne suka tara waxannan kayayyakin. Dungurawa sun ga abin mamaki don sun rasa maqasudin abin da Turawa ke nufi da wannan abu.

Malam Tanimu Zariya ne ya ba da wannan labari da ya ji, a wajen Dungurawa da suka zo Kaduna. An jima ana ba da wannan labari wanda ya zama tambari a garin Kaduna. Malamin ya ce:

"Ana cikin wannan hali, sai ga wani malami mai suna Malam Isa ya iso, nan da nan sai suka ce da shi ya shiga wannan xakin na jarabawa ya fito ya ba su labari. Shigar Malam Isa ke da wuya, sai ya fito ya ce da su "na ga Tarkace. " Jin wannan kalami, sai Turawa suka ce ya faxi gaskiya ai idan abubuwa iri-iri suka wuce biyu, ai sun zama ' "tarkace. " Turawa suka ci gaba da tambayar Malam Isa da cewa, "Me wannan abu yake nufi "? Malam Isa sai ya ce, "Wannan yana nufin zamanmu a wannan wuri, wato wancan mutum ya taho daga Kano, wancan daga Zariya da Ilori ko Bida, wannan kuma daga Kwantagora ko Ogbomosho ko Enugu, a taqaice dai qabilu daban-daban sun tarkatu a wannan garin. "[1]

Sai Turawa suka yi mamakin basira da ilhama da ilimin da Allah Ya bai wa Malam Isa, suka yaba masa, sannan suka ce daga wannan ranar shi ne Sarkin Alaron Leburorin Hedkwatar Dungurun. Malam Isa yaci sarautar Alaro a cikin shekarar 1905.

Aikin Sarkin Alaro yana da yawa, shi ne zai kawo wa Baturen aiki yawan leburorin da yake buqata. Idan za a biya leburori albashinsu, to, dole ne Malam Isa ya tabbatar da kowane lebura ya sami haqqinsa. Wannan qasaitaccen aiki ne idan aka yi la'akari da cewa waxannan dubban leburori sun bambanta ta qabila da al'adu, don haka shugabancinsu zai yi wuya matuqa. Da aka samu shugaba da isassun alaro, sai aka shiga aikin shimfixa hanyar jirgi da zai haxa Baro da birnin Kano.

A lokacin *Sir Frederick Lugard* ke gida, zuwa lokacin da aka naxa wanda zai gajesa, mulkin qasashen da ake yi wa Mulkin Mallaka yana hannun Mataimakin babban Jakada William Wallace ne (wanda jim kaxan bayan haka ya koma Sir William Wallace). Shi aka xora wa alhakkin saka wa a babban birninsa da lambar yabo ta *Order of St. Michael da St. George*, da kuma wata martabawar duk saboda yabawa da gwamnatin Ingila ta ba shi saboda biyayyarsa da aikace-aikacen da ya yi a lokaci hatsaniyar da aka yi a shekarar da ta gabata.

An sadaukar da shekarar 1906 ce musamman ga kammala shirye-shiryen karvar haraji (wanda ake karva qarqashin dokar En'e), kuma an samu gagarumar nasara a wannan vangare, har muqaddashin Babban Jakadan, a qarshen shekara ya iya ba da shawarwori ga Sakataren Qasa na a soke biyan haraji na ayari matafiya da lasisin kwale-kwale. An karvi wannan shawara, aka kuma yi aiki da dokar wannan gyara a farko-farkon Shekarar 1907, inda daga nan Razdan-Razdan suke samu qarin walwalar sadaukar da kai ga rangadin lardunansu da kuma tanadar da tsarin qungiya ta lardi. Hasarar kuxaxen shiga, ta zama babbar matsala saboda waxannan haraji biyu, a tsakaninsu suna samar da fam dubu arba'in (£40,000) a duk shekara. Aka yi fatar za a samu mafita ta hanyar qarin kuxaxen shiga na

[1] Hira da Malam Tanimu Zariya a Kaduna ran 4 ga Satumba 1984

haraji, na En'e, saboda kulawa kamar yadda ta kamata, wanda a yanzu Radan-Razdan za su samu damar aiwatarwa.

Zuwan Sir Percy Girouard

A farkon watan Janairu na shekarar 1907 aka yi sanarwar naxin Sir Percy Girouard K.C.M.G, D.S.O, wanda ya gaji Sir Frederick Lugard a matsayin Babban Jakada. Tashin hankalin da aka yi a Sakwwato a shekarar da ta gabata, ya sanya hankali ya karkata ga wani al'amari wanda Sir Frederick Lugard ya gabatar a rahotonsa na farko na shekara-shekara, wanda yake yawan ambato, wato matuqar buqatar da ake da ita ta gina titin dogo (jirgin qasa) zuwa cikin qasa. An kawo shewarwarin tsari daban-daban, gwamnatin Ikko ta kawo shawarwari a faxaxa titin jirgi da aka rigaya aka gina zuwa Arewacin Nijeriya daga tashar Ikko, titin ya xan yi nisa zuwa cikin Arewa, shi kuwa babban jakadan kudancin Nijeriya ya kawo shawarwari gina titin jirgin qasa daga tashar Calabar (tashar jirgin ruwa) zuwa tafkin Chadi.

Sir Frederick Lugard a rahotonsa na 1900 ya yi kiran a hanzarta tabbatar da tsari na reliwai. Ita kuwa Arewa kanta kamar yadda ya yi nuni tana buqatar titin jirgi daga gavovin kogin Neja zuwa Kano, amma ba na haxewa zuwa Ikko ba, wanda aiki ne da za a iya barinsa sai daga bisani. Ya ce kowanne yadi xayana titin jirgi daga Neja zuwa Kano wanda ya fi tsarin sufuri da ayari ke yi a kafa a yanzu zai bunqasa ci gaban kasuwanci. Za a yi amfani da hanyoyin ruwan wajen xaukar kayayyakin da jirgin qasa ya xauko daga cikin qasa zuwa gavar teku. Ya ce harkar ba ta tsaya ga batun kasuwanci kaxai ba. Ana buqatar sadarwa domin jin daxin mulki na ciki, da kuma domin tara dakaru da samar da kayayyaki.[1]

Wannan batu yana buqatar a hanzarta aiwatar da shi a shekarar 1903, kamar yadda aka yi a shekarar 1900, a lokacin da aka karvi ikon lardunan yankin Arewa. A rahotonsa na shekarar 1902, babban Jakadan ya sake jawo hankali ga buqatar da ake da ita ta hanzarta samar da reliwai, domin magancewahalhalu da ake sha ta sufuri da kafa hanyar jirgi wacce ke da tsada kuma babu gamsarwa wacce ita ce hanya xaya ta sadarwa da cikin qasa. Ya ce an yi safiyon wata hanyar a maimakon waccan. Wato daga Zungeru zuwa Zariya wacce Daraktan Ayyukan Jama'a ya gano. An kuma gano tashar ruwa a Neja, wacce za a iya gina hanyar jirgi mara nauyi wadda za ta bi ta Bida zuwa Zungeru, wanda ke nuna za a huta da tafiyar da ake yi ta ruwa da ke xaukar kwanaki goma ana yin ta.

A watan Nuwamban shekarar 1903 an turo wani injiniya da masu taimaka masa su biyu daga Ingila, su yi safiyon wani layin dogo daga Neja zuwa Zariya, a watan Yuni na 1904 aka kammala, inda aka samu hanya mafi sauqi. Sai dai kuxin

---

[1] Charles Orr. *The Making of Northern Nigeria*, Frank Cass & Co. Ltd., (1965), shafi na 183

da za a kashe, su ne suka zama kusan matsalar. Da ma yankin da ake yi wa mulkin tuni ya soma karvar agajin kuxi daga Ingila, kuma ba za a iya samar da wannan qarin kuxi na aikin gina titin jirgin ba wanda kuxi ne ba kaxan ba.

Saboda haka dole babban Jakadan ya haqura, ya rungumi aikin da ake kan yi na gina hanyar amalanke daga Zungeru zuwa Zariya daga kuxaxen da ake turowar, wanda a wannan lokacin ne aka vullo da tsarin sufuri ta amalanke, har sai lokacin da aka samu kuxaxen gina titin jirgin qasa. A watan Janairu na shekarar 1905, jerin amalanke na farko ya isa Zariya daga Zungeru, inda aka samu sauqin wahalar sufuri da qafa na xan wani lokaci. Ko da yake idan damina ta kankama amalanken ba sa iya zirga-zirga. A lokacin rani na shekarar 1905 zuwa 1906 an yi duk kan qoqarin da za a yi domin tsara wani qwaqqwaran tsari na sufuri. Aka shigo da direbobi da ire-irensu daga Indiya, kuma suka zama masu matuqar amfani; aka kafa daffo-daffo na samar da abincin dabbobin dake jan amalanken: da likitan dabbobi da aka baiwa sashen. Duk da dukkan wannan qoqari da aka yi, sufurin ta amalanke har tasa da wancan tsohon tsari na xaukar kaya ba ta taka kara ta karya ba.[1]

An san cewa Sir Percy Girouard, wanda babu wanda ya kai qwarewarsa a vangaren harkar reliwai (sufurin jiragen qasa), ya samu umurni na musamman na ya binciki lamarin tsarin reliwai, ya kuma miqa rahoto cikin gangawa. Jin kaxan bayan isarsa yankin da ake yiwa Mulkin Mallaka a watan Afrilu na shekarar 1907, ya ziyarci Zariya da Kano, ta bin titin amalanke, inda ya komo ta wata hanyar; da kuma xibar qasa ta kusa da Neja domin tantance yiwuwar samar da hanya ta sufuri ta ruwa. A watan Mayu ya aike gida wajen Sakataren Qasa cikakken bayani a kan dukkan wannan batu, tare da shawara a kan tsarin da yake ganin ya fi dacewa da yanayin da ya gani. Ba tare da vata wani lokaci ba, a watan Agusta na 1907 aka aiko masa da umarni daga gida, na an ba da izinin gina layin dogo daga Baro a Neja zuwa Kano, mai nisan mil xari uku da hamsin (350). An yi kintacen za a kashe fam dubu xari biyu da hamsin wato kwata miliyan, Layin dogon kuma ya zama irin na Ikko (qafa uku da inci shida) wajen nauyi da faxin qarfen titin dogon, kuma ya zama shi ne irinsa na farko. An kawar da batun matsalar kuxi ta wani shiri da aka yi inda yankin Kudu zai samar da kuxaxen (wanda aka haxe shi da Ikko), waxannan kuxaxe daga kuxaxen shiga da ake samu daga gudunmawa ta shekara-shekara daga Kudanci zuwa Arewacin na kuxaxen shiga na kwastam.[2]

Har ila yau, a wannan lokacin aka baiwa gwamnan kudancin Nijeriya izinin ya tura titin reliwai na Ikko har sai ya sami mahaxa da reliwai na Arewa da ba ta yi nesa daga Zungeru ba. Da hakan ne za a kafa hanyoyin sadarwa ta reliwai

---

[1] Charles Orr. *The Making of Northern Nigeria*, Frank Cass & Co. Ltd., (1965), shafi na 183

[2] *Ibid*, shafi na 185

tsakanin Kano da gavar ruwa ta tashar Ikko, da kuma wata hanyar ta Baro zuwa Neja. Sashen ayyuka na jama'a na Arewacin Nijeriya ne zai gudanar da gina reliwain na Arewa, inda za a qara yawan ma'aikata ta hanyar qara yawan injiniyoyi, da masu safiyo da sauran qwararrun jami'ai; sannan ita kanta gwamnatin Ingila za ta ba da aron wasu manyan injiniyoyinta, da albashinsu daga cikin kuxin da aka ware wa reliwai.

Hanyar Jirgin Qasa

Birnin Kano na da nisan mil xari bakwai (700 miles) daga teku, saboda haka in za a yi sufurin kayayyaki masu yawa, musamman gyaxa da auduga zai wahalar sosai. Ita wannan hanyar jirgi, Allan Mcphee ya yi wa laqabi da "Gyaxa ta qirqiro hanyar reliwai mai kyau cikin sauki. " Amma wani abin mamaki shi ne duk da kasuwar da auduga ta yi, ita ce ta haifar da shimfixa wannan hanya sai suka yi kicivis da kasuwar gyaxa. Arewa sai ta zama nagge daxi goma, ga qasar Ingila.

Wanne ne ba wacce ce ba, audugar ce ko kuma gyaxa? Kasuwar auduga sai ta kawo rububin kwaso ta. A wani rahoto a kan Kano, Turawa suka rubuta cewa: "A kowane lokaci saboda gyaxa mai albarka arziqin wannan qasa, na qarqashin sawunmu. " Saboda haka sai kasuwannin gyaxa da audugu suka assasa shimfixar hanyar jirgi.

A farkon shekarar 1905, sai Mista Malborough ya ba da umarni ga BCGA da ta fito fili ta bayyana wa jama'ar Ingila shirin aikin jirgi. A dalilin haka, a cikin watan, mayu na shekarar 1906, sai aka ta da wata babbar qungiya ta 'yan kasuwa qarqashin jagorancin *Lord Derbi*. Ita wannan tawagar 'yan kasuwa *Chambers of Commerce* ta qunshi; 'yan Majalisa sittin da huxu (64), da "Mayors " wato Magajin Gari guda talatin (30), da wakilan cibiyar kasuwanci guda ashirin da uku (23) da "Moor da Lord Malborough. " Ita wannan muhimmiyar qungiya ta sadu da shugaban qasar Ingila domin a tattauna a kan Nijeriya ta Arewa da arziqinta.

Firayim Ministan Ingila *Cambell-Bannerman* ya karvi wannan tawaga; tare da *Chancellor of the Exchequer Herbert Asquit*, da Sabon Sakataren renon Qashashen Ingila, *Lord Elgin* da *Winston Churchill*. An haxu za a yi taro a kan Arewacin Nijeriya mai ximbin arziqi da kuma yadda za a kwashi ganimar arziqinta. Abin alfahari shi ne wannan taro ya nuna muhimmacin arziqin Arewa, wanda ba kamarsa a Afirka. Da wannan arziqin ne aka raya Nijeriya kafin ta kai ga samun man fetur. Kakakin tawaga ya ce: "an fahimci babu hanyar sadarwa a yanki mai albarkar auduga, saboda haka ya kamata a samu matsaya a kan Arewacin Nijeriya, wadda ka iya baiwa Masaqar *Lancashire* wata madafa. A sakamakon wannan tattaunawa ne ya sa a watan Agusta na shekarar 1907, Xan Majalisa Winston Churchill ya bayyana a Majalisar "House of Commons," za a shimfixar hanyar jirgi cikin hanzari zuwa Kano.

Wannan bayani ya sami faxin ra'ayoyin jama'ar qasar Ingila. Ya kuma qara fito da Arewacin Nijeriya wata qasa babba mai ximbin arziqi, kamar yadda ake ganin yankunan da ake samun man fetur, a Nijeriya a yanzu. Saboda haka kowa na faxin ra'ayinsa game da wannan aiki sai Editan jaridar "The Times, " wata mashahuriyar jarida a Ingila da qasashen Turai, ya yi sharhi kamar haka: "Abu ne mai sauqi a yi tsamnanin idan aka cika Arewacin Nijeriya da auduga za ta samar da issassar auduga a nan gaba. A yi mata wannan hanyar jirgi yanzu da kuma wasu a nan gaba. Wato abin nufi shi ne kuxin da aka qiyasce kashewa ya dace sosai, amma abin takaici shi ne aikin da zai xauki tsawon lokaci. "

A ire-iren kowa faxi albarkacin bakinka, da ya biyo bayan maganar Mista Churchill wanda ya bayyana umarnin gwamnati, na shirin shimfixa hanyar jirgi sai ra'ayoyin jama'a ake ji ta ko'ina. Mutanen Ingila na murna da samun garavasa mai amfani a lokacin da qasar ta shiga qaqa-nikayi wajen neman auduga. Lallai, wannan wata Rahamar Allah ce, da ta zo masu daga Arewacin Nijeriya. Ita kuwa qungiyar BCGA, baki har kunne saboda murna da farin ciki, cewa ta yi: "Wannan rana ce mai muhimmanci sosai. Kano, ta zama Makka ga masaqar Lancashire, za a kuma haxa ta da tattalin arziqi na duniya. "

Allah Maxaukaki, ke xaukaka wasu mutane a kan wasu; Ya xaukaka wasu dabbobi a kan wasu; Ya xaukaka wasu ma'adinai a kan wasu; Ya kuma xaukaka wasu kayayyakin gona a kan wasu, a lokuta daban-daban, domin Shi ne Mai kowa Mai komai. Kwaram! Sai ga Allah Ya xaukaki auduga har manyan qasashen Turai na nemanta kamar ruwa ajallo.

A lokacin da kayayyakin gona ke da daraja arziqin Nijeriya, a Arewa yake, da kuma wannan arziqi aka gina ta har ta qasaita. A kuma wancan lokaci ne, Arewa ta zama akushin tuwo mai hannu da yawa, kowa yaci ya qoshi ba tare da wata tsangwama ba, arziqi ne yau a gidanka, gobe a gidan wani. Amma da samun man fetur a Kudu, sai 'yan Kudu, musamman yankunan man fetur, sai idonsu ya rufe. Har ma sai gori suke wa 'yan Arewa, suna cewa, "ai Arewa ba ta da arziqin komai sai jigawa wato hamada. " Abinka da qananan mutane, tuni sun manta da alherin da aka yi masu jiya. Inda mutunci, ai wanda ya yi maka kan kara, kai sai ka yi masa na itace.

Yau aka sani ba a san gobe ba. Allah Kaxai Ya san arziqin da ke damvare a qarqashin jigawa. Haka kuma a lokacin da kuza wato (iron ore) ke tashenta, babu wanda ya tava tsammanin darajarta za ta yi qasa, kamar yanzu. Babu wani abu tabbatace sai Ikon Allah. Arziqin mai, ba mai dauwama ba ne. Masana kimiyya na cewa a bi sannu, wata rana na zuwa, sai, ruwan sha ya fi man fetur tsada da daraja, da kuma wuyar samuwa.

A lokaci da kusan kowane manomi a Arewa yake noma auduga; a kusan kowa ne gida ana yin kaxin zare da abawa, babu wanda ya tava mafarkin auduga za ta kai darajar da ta kai a lokacin zuwan Turawa. Sai ga shi darajarta da darajar gyaxa

da sauran kayayyakin gona da ma'adinai da na dabbobi sun sa za a shimfixa hanyar jirgi daga Baro zuwa birnin Kano.

An kuma yi wannan aiki ne saboda a hanzarta zirga-zirgar sojoji; a sauqaqa kwasan arziqin gona na Arewa da a sauqaqa kwasan kuza da ke qasar Filato. Amma kamar yadda *Sir Rex Niven,* ya ce, 'an shimfixa hanyar jirgi daga Baro saboda kwasar auduga. An fara shimfixa kwangirin jirgi daga Ikko zuwa Abeokuta a cikin shekarar 1898. Hanyar ta kai garin Ibadan a cikin shekarar 1901. *Sir William Macregor,* Gwamna a Ikko shi ne ya yi bikin buxe hanyar jirgi daga Ikko zuwa Ibadan a ranar 4 ga watan Maris na shekarar 1901. Wannan hanya ta iso garin Jebba a cikin watan Satumba a shekarar 1908.

Saboda arziqin kayayyakin gona da yake maqil a Arewa da kuma fahimtar samuwar auduga mai kyau a qasashen Hausa, sai ya zama tilas a yi hanyar jirgi wadda za ta haxe babbar tashar jirgin ruwan Arewa, wato Baro (da ke bakin kogin Kwara) da birnin Kano. Wannan zai sauqaqe wahalhalun jigilar buhunan auduga daga Arewa da kayayyakin gona suka iso garin Baro sai a loda wa jiragen ruwa a yi waje da su zuwa Ingila ta Fokados (Forcados) da Burutu da suke bakin Teku.

Har ila yau, Arewacin Nijeriya na da arziqin zinare wato (Gold) mai yawa da daraja. A yankin lardin Neja inda ake haqar wannan zinare sai aka sa masa suna "Mineral Area ." Garin da ake haqar wannan zinare a wannan yanki kuma sai ya samu suna "Minna " daga kalmar "Mineral ." A zamanin Mulkin Mallaka wannan gari ya yi tashen arziqi saboda zinaren da ake samu a garin Minna, madaran zinare ne mai daraja da tsada. Don haka ne Turawan Mulki suka maida wannan gari wajen haqar zinare mai albarka, sun kuma kwashi wannan zinare mai yawan gaske. Saboda yana da daraja da tsada a qasar Ingila. A daliliin haka ne aka shimfixa hanyar jirgin qasa zuwa Minna.[1] An kafa hanyar jirgi a sassa daban-daban a Arewa saboda jidar arziqin gona da na ma'adinai a Arewa.

Kafin a fara muhimmin aikin shimfixa hanyar jirgi da za ta haxa Baro da Kano, sai da aka yi babban shiri aka kuma tara xaruruwan leburori daga sassa daban-daban na lardunan Arewa. An kuma haxe hanyar jirgi tsakanin garin Jebba da Dungurun. Zirga-zirgar jirgi ta samu tsakanin Jebba da Minna cikin farkon watan Janairu na shekarar 1912. Ranar 8 ga watan Agusta na shekarar 1907, gwamnatin Mulkin Mallaka ta zartar da a shimfixa hanyar jirgi daga Baro zuwa Kano.

Ana samun izinin wannan aiki sai aka mike tsaye gadan-gadan inda duk wanda aikin ya shafa ya dage. Aka tsara dukkan kayayyakin da ake buqata aka tura Ingila, aka gudanar da safiyo, aka soma ginan qasa. Aka kira ma'aikatan siyasa su samar da ayyukan qwadago ta hannun Sarakuna da qananan jami'ai, inda

---

[1] Ahmad Abdulqadir, *Gambo Sawaba: Kallabi Tsakanin Rauwuna*, Ganuwa Publishers Zaria (1993), shafi na 83.

aka tsara yadda za a dinga biyansu. An jawo kowanne sashe ya agaza, shi kansa babban jakadan ya nuna abin koyi inda shi da kansa ya jagoranci shirye-shiryen wannan aiki. A watan Yunin shekarar 1908, watanni shida da soma wannan aiki, an kammala safiyon mil xari da arba'in (140), aka kuma soma safiyon qarin wani mil xari da saba'in (170), da taimakon jami'ai daga dakarun WAFF da sauran sassa; aikin ginan qasa ya zarce nisan mil xari (100); kuma an yi shirin karvar tan dubu ashirin da biyar (25,000) na kayayyaki a Baro. Sarakunan yankunan suka nuna matuqar sha'awarsu a aikin, inda suke ziyartar wuraren, da ba da kowanne taimako ta wajen shirya samar da laburori.

A dai wannan lokaci ne, aka yi qoqarin kyautata kogin Neja daga gavarsa zuwa Baro. Wani safiyo na qarafunan titin jirgi daga wannan mahaxa zuwa wancan wanda ya haxa da wajen kwanciyar yashi da ke kawo cikas ga aikin, in an haxa ba su wuce mil uku zuwa huxu ba a tsawon mil xari huxu (400). Saboda haka aka yi odar wata na'ura ta musamman ta yashe hanya da ake sa ran samar da qafa huxu ta qarfen a tsawon shekarar da zai taimaka wucewar qafar jirgi, Idan wannan tsari ya yi nasara za a iya amfani da Neja wajen sufurin kayayyaki, zuwa cikin qasa, ko kuma daga cikin qasa zuwa gavar ruwa. Domin taimaka wa sufurin kayayyaki, an yi odar wasu manyan kayayyakin sufuri guda uku da wasu marasa nauyi guda goma sha-huxu a qarshen 1907, kuma a shekarar da ta biyo baya kayan suka iso.

Inganta hanyoyin sadarwa daga gavar teku zuwa cikin Arewacin Nijeriya ba ta yo usuli ne saboda buqatu kaxai ba har ila yau batun ya taso ne saboda fatar da ake da ita nan gaba, cewa qasar za ta zama gagarumar vangaren fitar da auduga zuwa qasashen qetare. Zariya wacce ita ce cibiyar noman auduga, tana da nisan mil xari shida daga gavar teku, kuma mil xari uku (300) daga gavar kogin Neja mafi kusa. Vangaren masana'antar haqar kuza ita ma tana buqatar kayayyaki na sufuri, na fitar da tama (kuza) da kuma shigo da injina. Yankin haqar ma'adinan yana a tsaunukan Filato a Yamma da lardin Bauci. A kai wajen daga gavar teku na buqatar babban jirgin teku da zai bi kogin Neja har zuwa Lakwaja, nisan mil xari uku da *arba'in* (340), daga nan a hau jirgin ko kwale-kwale a koma wata tashar jirgi ta Loko, mil xari da goma (110) har zuwa Binuwai, daga Loko sai mil xari biyu (200) zuwa yankin haqar ma'adinan.

In babu kayayyakin sufuri, leburori ne za su xauki dukkan waxannan kayayyaki su niki wannan nisan tafiya, kuma ga nauyin kowanne kaya ya kai awon nauyi sittin da biyar, wanda ba qaramin kaya ba ne. Idan aka gina hanyar jirgin qasa daga kogin Neja zuwa Kano, za a samu sauqi wajen haxe layin dogon da wuraren haqar ma'adinan mil xari (100) zuwa Gabas, wanda hanya ce mai sauqi da arha zuwa gavar teku.

Yana da wahala a iya zayyana muhimmancin wannan titin jirgi da ake matuqar buqatarsa ga wannan yanki da ke qarqashin Mulkin Mallaka wata dama

ce ga 'yan qasa su nunawa kasuwar duniya amfanin gonarsu, da kuma musaya da kayayyaki da aka sarrafa da sauran kayayyaki na qasashen qetare. A matsayin hanya ta kawo wayewar kan titin jirgi da ya haxe cikin nahiyar Afirka da gavar teku, zai taka muhimmiyar rawa, da aza tubalin ci gaba gina reliwai a sabon yanki Afirka mai yanayin zafi na da sakamako na wayewar kai. Zai tattaro al'umomi wajen da ke nesa zuwa waje xaya, da koyon tsarin aiki na samun albashi a kullum da duk mako, da amfani da kuxi. Da fahimtar tasirin qwadago kan aikin ginan qasa ke da shi a zukata da kuma halayyar arne wanda bai ci gaba ba, da fahimtar wani abu na musaya wanda ke aukuwa a ra'ayoyinsa, dole wani ya soma saninsa a inda yake keve a qauyensa, da kuma kallonsa bayan 'yan makonni yana aiki a sansanin aikin reliwai. An zaqulo fasaha da basirarsa, keve kansa da ya yi da ta kau, tsoronsa ya vace, ya waye tare da mutunta kansa.[1]

Sir Percy Girouard ya tafi lifi a farkon shekarar 1908, ya dawo a watan Yuni na wannan shekara. Kafin qarshen shekara har ya yi rangadin qasashen Hausa inda ya sadu da Sarakuna, ya kuma faxa masu cewa gwamnatinsa tana da niyya da shiri-iri xaya da gwamnatin da ta gabata. Saboda haka tsarin mulki ba zai sauya ba.

A watan Afrilu na shekarar 1909 aka sauya muqamin *High Commissioner* zuwa Gwamna kuma Shugaban Qasa, a wannan lokacin ya koma Ingila lifi sai *Sir William Wallace* ya zama Gwamna mai riqo. Ana nan sai ga labari tafe cewa likkafar *Sir Percy Girouard* ta yi gaba, an naxa shi gwamnan Gabashin Afrika saboda haka ba zai komo Nijeriya ta Arewa ba. Amma za a daxe ana tunawa da shekaru biyu da ya yi yana mulkin wannan qasaitacciyar qasa wadda ya taimaka wajen ciyar da ita gaba. An kuma ji rashin sa sosai. Duk da haka *Sir William Wallace* ya ci gaba da mulkin wannan Yanki har ya zuwa watan Disamban shekarar 1909 a lokacin da aka naxa *Sir Henry Heskett Bell*, K.C.K.G a matsayin sabon gwamnan Arewa. Saboda haka a cikin xan Qaramin lokaci qasa da shekaru uku Gwamnoni huxu suka yi mulkin Arewa.[2] *Daga Lord Frederick Lugard* a shekarar 1906 sai *Sir Percy Girouard* a shekarar (1906-1909) daga shi sai *Sir William Wallace* (Afrilun shekarar 1909-Disamban shekarar 1909), sa'an nan sai *Sir Heskett Bell* a shekarar 1910, daga shi sai Gwamna Lugga ya dawo ya karvi mulkin Arewa, amma a matsayin gwamnan Nijeriya, ya ci gaba da shirye-shiryen aikin hanyar jirgi.

Wannan bayani ya fayyace dalilai da amfanin da hanyar jirgin qasa (Baro zuwa Kano) zai kawo. Haka zalika, ana iya gane hangen nesa da Sarakunan Arewa suka nuna wajen ganin an aiwatar da wannan aiki da gaggawa. Sa'annan za

---

1 Charles Orr, *The Making of Northern Nigeria*, shafi na , 186-189

2 *Ibid*., shafi na 192-193

a iya gane gudunmawar da Sarkin Alaro Malam Isa da rundunar Leburorinsa suka bayar da asubahin fari, a gina Sabuwar Nijeriya ta Arewa.

Bikin Daba a Dungurun

Shirye-shiryen aikin shimfixa hanyar jirgin Baro zuwa Kano, ya sa Turawan Mulkin Mallaka aikawa Sarakunan Hausa saqon cewa da su aiko masu da mazaje majiya qarfin tuwo domin su zo su tallafi gagarumin aikin da zai bunqasa arziqin qasarsu. Saboda a samu jama'a sai Turawa suka shirya yin bikin 'Daba' a garin Dungurun hedkwatar Arewa, wato hawan bangirma.

An fara bikin Dabar a cikin watan Fabrairu na 1908. Sarakunan qasashen Hausa tare da xaruruwan jama'a sun hallara wajen wannan biki a hedkwatar Arewa. An yi biki cikin farin ciki da annashuwa.

Sarakunan Hausa sun taimaka sosai wajen turo leburori daga ko'ina a cikin Arewa. Samun isassun ma'aikata ya sa aka duqufa wajen shimfixa kwangirin jirgi mai nisan mil xari uku da hamsin da shida (356), wanda ya faro daga garin Baro a cikin watan Agusta 1907 ya kai birnin Kano a cikin watan Maris na 1911. Wannan muhimmin aiki ya yiwu ne saboda samun nagartattun leburori tare da kyakkyawan goyon bayan da Sarakunan qasashen Hausa suka bayar. Sarkin Zazzau Aliyu Xan Sidi da Sarkin Kano Abbas sun yi matuqar qoqari wajen kammala wannan muhimmiyar hanya.

Bayan an gama Hawan Bangirma, sai Sarkin Zazzau da ayarinsa, suka wuce zuwa garin Bida, inda Sarkin ya halarci bikin buxe wani yankin farko na hanyar jirgi da a haxa Baro da Badeggi. Ya dawo Baro inda ya duba ayyukan wakashof relwe wato (Railway Workshops) da sauran ayyuka makamantansu. Sarkin ya koma Zariya a qarshen watan Fabrairu na shekarar 1908.[1]

Sarkin Zazzau Aliyu Xan Sidi ya samu damar ganin kayayyakin aikin jirgi iri-iri waxanda suke sabbi ne a Arewa. Waxannan kayayyaki babu shakka sun baiwa jama'a mamaki don babu wanda ya yi mafarkin ganin targunan jirgi da kayan aiki irinsu a wancan zamani. Saboda haka ne ma Sarkin ya tashi tsaye sosai, ya ga wannan aiki ya cimma nasara. Amma duk da gudunmawar da Sarakuna suka bayar wajen ganin aikin ya tafi sosai, sai da aka samu cikas. Aikin diga ko kuma aikin shimfixa kwangirin jirgi ya samu 'yar tangarxa lokacin da aka fara, an kuma xauki matakai da dama wajen shawo kan matsalolin da suka kawo wa aikin cikas.

Xaruruwan leburorin da Sarakuna suka turo, sun taru jingim a Dungurun. Waxannan bayin Allah da aka turo sun yi wa qasarsu bauta wadda za ta kawo ci gaban garuruwan su, sai suka yi tunzuri suka yi biris da aikin. Har masu so su yi tawaye saboda irin jita-jitar da ke watsuwa game da aikin diga ko shimfixa hanyar jirgi.

---

[1] Zaria Provincial Gazetter, shafi na 30

Mutane na jita-jitar cewa ai aikin diga zai kawo fashewar gari da qauye. Waxansu kuma su ce haramun ne irin wannan aiki na Nasara, alama ce ta tashin duniya. Jama'a sai kowa faxin albarkacin bakinsa yake yi. Wannan ruxani ya sa leburori 'yan diga suka qi yin aikin.

Al'amari ya cave, ba don komai ba sai don rashin fahimtar amfanin wannan hanya tare da jahilci. Mutanen wannan lokaci ba su da ilimin Nasara, saboda haka shawo, kansu abu ne mawuyaci sai da dabaru da lafazi mai qarfi. Shigowar kayayyakin zamani waxanda ba a tava mafarkinsu ko jin labarinsu ba sun kixima kakanninmu, don haka masu cewa tashin duniya ne ya gabato suka kusan jan ra'ayinsu.

Waxanda suka fahimci amfanin hanyar jirgin da kuma hangen za ta bunqasa qasashensu su ne Sarakunan wannan lokaci. Su ne suka xauki aikin da muhimmanci sosai. Sarkin Zazzau Aliyu Xan Sidi tare da Sarkin Kano Abbas sun yi namijin qoqari wajen shawo kan jama'arsu da su yi wannan aiki. Ta waqe an fi samun jawo hankalin jama'a ta hikima da basira, don haka sai Sarkin Zazzau wanda ya ga aiki da kayan aiki ya kuma fahimci amfanin wannan hanya sai ya wallafa waqar Diga.

Tunzurin leburorin aikin hanyar jirgi, wato 'Yan diga tare da dagulewar al'amarin wannan aiki, sun sa Sarkin Zazzau Malam Aliyu Xan Sidi ya hau takanas shi da jama'arsa zuwa garin Baro domin gane wa idanuwansu abubuwan da suke faruwa game da aikin hanyar jirgin. A kwana a tashi har suka isa can wajen aikin. Zuwan su can kuwa ya qarfafa wa 'yan diga zuciya, ya kuma rage irin jita-jitar da ake yi a qasa game da aikin. Sarki Malam Aliyu Xan Sidi sai ya wallafa waqa musamman ta wannan aiki, ya sa mata suna 'Waqar-Diga'

Wannan ita ce hanya mafi dacewa ta shawo kan al'amarin. A cikin waqar digar, Sarkin ya nuna basira matuqa, ya kuma nuna fahimtar jama'arsa da yadda zai shawo kansu ya kuma tafi da su cikin lumana. A wannan waqe, Sarkin ya fito da matsalolin da suke addabar leburorin aikin, ya zama mai rarrashinsu, yana kuma kwaxaitar da su alherin da za su samu. Wannan abu ya qara masu qwarin gwiwa sosai. Wajen ruxanin da jama'a ke kawowa a kan wannan aiki, Sarkin ya ce a cikin baitocin waqar Diga:

4. Ga Allah tutur duk nufi ke tafe,
   Ina bisa roqo maraice da safe,
   Shi tsarshe mu sharrin da duk ke tafe
   Da munka ji an ce yana tafe,
   Qwarai mun ji tsoron sa aikin diga.

Ban da jita-jita, wahalar aikin digar kansa ya isa ya sa xan Diga ya gudu. A nan ne Sarkin ya kawo wannan abu:

24. Da sanyi da zafi da iska da rana,
Suna bisa kanmu tutur ba mu kwana,
Muna qoqari mu gama 'yan uwana,
Rashin kau da kai bisa aikin wuyana,
Kusan tsanani agga aikin diga.

Wajen al'ajabin da mutanen wannan lokaci suka gani saboda shigowar kayayyakin aiki irin na zamani, Sarkin ya ce:

18. Daxa ka ga an kama aiki da safe,
Ana bisayi wansu nan tafe,
Jiragen qasa ga su xauke da qarfe,
Fa ya ajaban xan uwa na ga qarfe,
Yana yanke qarfe ga aikin diga.

Ga masu watsa jita-jita wajen wargaza wannan shiri. Sai mawaqin ya nemi jama'a da waxanda suka kai hankalinsu nesa da su natsu don harin mahara ba shi motsa daji ballantana aikin diga ya kawo fashewar karkara. Shahararren mawaqin ya ce:

25. Ilahi ka tsarshemu kowane sharru,
Ya rabbi don Shehu don kuma Nuru,
Zancensu kullum shi ne sharru,
Da mata da yara da kau ashararu,
Su kan ce qasa ta fashe don diga.
26. Ina tammaha babu mai yin huruji,
Gida nai batun ga na qarya ku barji,
Ku saurari zancen qwarai kai haraji,
Harin mahara ba shi motsar da daji,
Bare karkara ta fashe don diga.

Ya kuma kwaxaitar da leburorin aikin samun kuxi wanda ya kira da 'matar diga'. Ai samun mallakar matar diga sai wanda ya riqi diga. Mawaqin ya ce:

49. Fara ce misalinta kok ganta duk,
Shina son ta ai babu mai qinta duk,
Cikin jama'a zamanin yanzu duk,
Tana nan da zane a kwivinta duk,
Tana da qaho qirji matan diga.
50. Haqiqa masoyanta na ta bixanta,

Waxansu fatauci suke su riqe ta,
Waxansunsu nomasuke su riqe ta,
Masoya gareta barori gareta,
Gidanta na qarfe na sa ai diga.[1]

Ta amfani da hikima da lallama Allah Ya taimaka an samu shawo kan dagulewar al'amarin. Waqar diga ta taimaka gaya wajen faxa da tunzuri tare da ruxanin da suka taso. Mata da yara sai rera waqar suke yi. Aikin diga sai ya zama kamar aikin gayya, hankalin mazaje ya tashi wajen neman mallakar matar diga (Kuxi). Samun matar diga ko a wannan lokaci sai wanda ya riqi diga. Wannan waqar ta qara samun leburori a aikin, hanyar jirgi daga Ikko zuwa Kano sai ta samu cikin hanzari. Waqen Sarkin Zazzau, Malam Aliyu Xan Sidi "sakaina mai iya ruwa " ta taimaka gaya wajen tabbatar da samun wannan hanya.

Aikin Diga

Kafin mu ji irin murna da bukukuwan da Sarakunan Arewa suka yi don isowar jirgi qasashensu. Yanzu kuma sai mu duba mu ga yadda mazaje wato leburori da ma'aikata suka sha jar wuya wajen wannan aiki, "ku san tsanani agga aiqi diga!

Babban Injiniyan da ya tallafi wannan aiki kuwa shi ne babban Kwamishina, Sir E.P.C. Girouard, qarqashin shugabancin Mista Eaglesome wanda shi ne Daraktan Jirgi da Ayyuka. Shi wannan babban Bature, Gwamna Lugga ne ya naxa shi, saboda qwarewarsa wajen aikin hanyar jirgi. *Sir Girouard*, ya tava zama babban Injiniyan *Lord Kitchner* lokacin da ya shimfixa masa hanyar jirgi da ta ratsa Sahara ta faro daga garin Walfa zuwa Khartoum ta qasar Sudan. Don haka qwararre ne wajen shimfixa hanyar.

Leburorin wannan aiki, kamar yadda aka yi bayani a baya, Sarakuna da shugabanni na qasashen Hausa ke turo su. Misali, idan aka aza wa magidanci waxansu kuxin da ba zai iya biya ba (ya kuma kasa biya), to, wajibi ne gare shi ya ba da ma'aikacin da za a tura don aikin hanyar jirgi. Wani lokaci ma Makarantun Allo ake bi ana turo gardawa don su zo su yi wannan muhimmin aiki. Da haka ne aka tara xaruruwan ma'aikata.

Idan Baturen safiyon aikin hanyar jirgi ya yi aikinsa, dole ne hanyar ta tafi a miqe, ko kuma ta lanqwasa a hankali ta yadda kwanar ba za ta kawo haxari ba. Manya-manyan itatuwan da ke kan hanyar ko duwatsu, sai an kau da su sa'an nan hanyar a fitar da ita ta yi lebur sosai.

---

[1] *WaQoQin Aliyu Xan Sidi*, Sarkin Zazzau, The Northern Nigerian Publishing Company Zaria (1980), shafi na . 26-29

A wannan lokaci fa, babu kayayyakin aiki irin na zamani, abin da waxannan leburori suka sani kuma suka dogara da shi, shi ne qarfin tuwo. Da qarfin tuwo suke sarar itatuwa, suke sassabe sagagi, suke fasa duwatsu, sa'an nan kuma su yi amfani da qarfin na su su xauko qarfen dogo. Injunan da ake amfani da su ba su da yawa a wannan lokaci. Aikin Turawa shi ne ba da umarni.

Saboda aikin ya rabu kashi-kashi, sai a raba leburori rukuni-rukuni. Kowane rukuni kuma aikinsa daban, akwai 'yan nakiya da 'yan fasa dutse da masu kwaso qasa da duwatsu da 'yan xauko qarfen dogo da sikwati, sa'an nan kuma masu sarar itatuwa da 'yan aikin kwalbati duk rukuninsu daban-daban.

Idan an tarar da qungurmin jeji, sai 'yan sarar itatuwa su shiga aikinsu na sheme itatuwa da nome hanyar ta fito sosai, ta kuma yi lebur. Su waxannan ma'aikata suna aiki suna ihu da kixa domin su firgita namun jejin da ke cikin dawa. Amma duk da wannan mataki da suka xauka, da yawa daga cikinsu na gamuwa da muggan namun jejin da ke cikin dawan, har ma wani lokaci su kan yi wa leburori muna nan raunuka ko masu hallaka su.

Idan hanya ta bi ta kan manyan duwatsu kuwa, sai a kira 'yan nakiya. Su 'yan wannan qungiya sun qwarewajen buga nakiya. Idan an kimanci yawan nakiyar da ya kamata a buga, sai ma'aikatan su shiga haqar dutsen da wani qarfe mai xan kauri da tsini, ana kiransa 'kwalaba'. Da wannan kwalabar ne sai su haqa rami mai zurfin qafa biyu zuwa uku. Bayan an gama haqawa, sai a sa nakiya a raminta kuma a tabbatar da ita nakiyar ta kama dam-dam a raminta. Da zarar kowa ya yi wannan abu, sai a busa usur fir! fir! ! Domin duk wani mutumi da ke kusa da wajen, ya gudu nesa, ya je ya yi kwanto, sai kuma a hana jama'a bin wajen da za a buga nakiyar. Kusan lokaci guda sai duk a cinna wa lagwanin nakiyoyin wuta. Da yin haka sai kowa ya zabura a guje ya tafi wani waje nesa ya yi kwanto. Cikin xan qaramin lokaci sai ka ji bum! bum!! Nakiyoyin sun buga, cikin wannan lokaci su waxannan ma'aikata su qirga yawan nakiyoyin da suka buga.

Idan akwai wata nakiyar da ta qi bugawa har tsawon wani lokaci, to, sai a yi hani ga jama'a da ma'aikata da kada kowa ya je wajen, sannan a kafa jar tuta a shiyyar wajen don nuna alamar wannan waje yana da haxari. Bayan kamar kwanaki uku, idan har nakiyar ba a ji ta buga ba, sai a je a dubo. Ana xaukar wannan mataki ne don tsoron kada a yi hanzarin zuwa wajen a tarar da za ta buga, in wannan ya faru sai jama'a su hallaka.

Idan nakiya ta buga sai ka ga duwatsu sun fashe sun kuma tarwatse, vangaren duwatsun kuma an yi jifa da su zuwa waje mai nisa. Saboda haka ne jama'a ke gudu su tafi waje mai nisa su yi kwanto. Duwatsun da suka fashe ana yin amfani da su don yin hanyar jirgi. Aikin 'yan fasa dutse ne su farfasa waxannan duwatsu don a baje su bisa hanyar jirgi. Ana tara duwatsun da aka fasa tsibi-tsibi, aikin masu kwasar duwatsu ne su zo su kwashe su.

To, amma kafin a xora dogon jirgi kuma, sai an tara qasa ta yi xan tudu kamar kunya, sa'an nan a kawo duwatsu a tula sosai, sai duwatsun sun fi qasar yawa sosai. Bayan wannan sai a kawo wani qarfe mai tsawon qafa 6, faxin qafa 1, gefen wannan qarfe kuma an xan lanqwasa shi, cikinsa kuma na da xan zurfin rabin qafa. Shi wannan qarfe da ake xora qarfen dogo bisansa, sunansa sikwati. Yana da wajen maxaurar qarfe a gefen dama da hagu.

Idan an tara qasa da duwatsu, sai a kifa cikin sikwati xin bisa. Haka za a xora bisa jerin sikwati dama da hagu, a sa maxauran qarfe a xaure kowane sikwati da qarfen dogon.

Bayan an xora qarfen dogo bisa jerin sikwati, kuma an xaure kowane sikwati da qarfen dogo, sai a sa ma'auni a auna don a tabbatar hanyar dogon ta yi lebur sosai. Idan hanyar ba ta yi lebur sosai ba, sai a xan caccaka dutse qarqashin sikwatin, in sikwatin ya yi tudu sai hanyar ta yi lebur sosai. Akwai wani ma'aikaci 'bita' mai kamar diga, amma ba shi da tsini, da shi ake yin amfani wajen mayar da hanyar dogo ta yi lebur sosai. Ma su wannan aiki na tabbatar da hanyar ta yi lebur, ana kiransu 'yan bita'.

Aikin 'yan bita shi ne duk inda hanyar ba ta yi lebur ba sai su zo su caccaka duwatsu qarqashin sikwati, sai ya xago kuma hanyar dogon ta yi lebur sosai.

In hanya ta bi ta kwalbati, aikin 'yan kwalabati ne, su kwava suminti da dutse su zo su yi daven kwalbati. Duk kwazazzaban wajen sai an haqe su sosai, sa'an nan a xauko aiki tun daga tushe. Idan aka yi rami mai zurfi sai a kawo suminti da yashi da dutse a cike sai ka ga kwalbati dandavavve ya fito sosai. Duk kuma wajen da aka ga alamar ruwa zai kwanta, sai a yi masa makwarari. Kowane aiki ana yinsa cikin hanzari, kuma ba tare da amaja ba. Aiki ne na wanda in an sa amaja a cikinsa, Allah kaxai ya san rayukan da za su salwanta.

Waxannan nagartattun ma'aikata sun iso da muhimmiyar hanyar nan Maqera da ke bakin kogin Kaduna, a cikin shekarar 1911. A wannan wuri ne aka yi 'yan gidajen ma'aikata. Leburorin da aka iso da su wannan waje ba za su isa gama ginin gadar jirgi a kogin Kaduna cikin hanzari ba, wannan ya sa Turawan aiki suka aika wa kowane Razdan da ke qasashen Hausa da su nemo gudunmawar leburori don a yi aikin gayya a kuma gama ginin gadar cikin xan qaramin lokaci.

Gina Gadar Jirgi

Saboda a kammala aikin wannan muhimmiyar gadar, wato gadar jirgin kogin Kaduna cikin hanzari, kowane Razdan da ke qasashen Hausa ya samo taimakon leburori. Sarakunan wannan lokaci sun taimaka da leburori da abinci da mata madafa abinci da makaxa da mawaqa don a yi wa wannan muhimmiyar gada aikin gayya. Malam Tanimu Zariya ya ba da labarin cewa:

Sarakunan da suka aiko da taimakonsu su ne: Sarkin Kano Malam Abbas da Sarkin Zazzau Malam Aliyu Xan Sidi da Mai Turare, Shehun Barno Garbai da Sarkin Bauci Yakubu Ida Sarkin Gwandu Halliru Audu da Sarkin Ilorin Sulaiman da Sarkin Bida Muhammadu Masaba da Lamixon Adamawa Zubairu da Sarkin Gwambe Buba Yaro. Taimakon waxannan Sarakunan ya hanzarta gama wannan aiki qwarai da gaske. Duk kusan kowane Sarki ya aiko da jama'arsa.[1]

Waxannan Sarakuna sai suka ba Hakimansu umarni da su turo mazaje, samari majiya qarfi. Hakimai suka faxawa Dagatai. Su kuma Dagatai suka faxa wa masu Unguwanninsu wannan umarni na Sarakuna da suka samu daga Razdan xinsu. Ko wani rukunin ma'aikata yana da nasa shugaba, wanda zai kasance amintaccen Dagaci ne ko amintaccen Mai Unguwa. Saboda ana kwaso su daga Makarantun Allo, ko gonaki; sai idan wannan rukuni ya sami aikin wata guda, sai a sake shi, wani rukunin ya maye gurbinsa. Da haka aka riqa yin, wannan jan aiki mai wahala. A wajen aikin gayyar an tara ma'aikata da leburori masu ximbin yawa.

Ko da yake Sarakuna da shugabanni sun taimaka wajen shugabancin leburori takan Dagatai da wakilansu, amma haqqin wannan shugabancin na wuyan Jami'i mai hulda da jama'a wato *Political Officer* da shi da Sarkin Alaro. Su ne suke tsara yadda sauran shugabannin za su taimaka wajen tafiyar da aiki da harkokin waxannan leburori. *Political Officer*, yana da ayyuka uku: tsara aiki da ciyar da ma'aikata da kuma biyan su haqqinsu.[2] Wannan Jami'i na tafiyar da waxannan ayyuka ne tare da Sarkin Alaro Malam Isa. Saboda shi ke tare da leburoirin, sun kuma amince masa sosai.[3]

Yanzu leburori sun hallara, an kama aiki tuquru babu ji-babu-gani, mazaje kam sun aikatu. Sai ka ga sun yi gungu misalin mutane maitan, kowane na sara da diga, masu kwasa su masun yi gungu, aiki suke yi wurjanjan. Mazaje masu kwavar suminti da dutse sun duqufa. Kai daga nesa in ka hange su, ka ce injuna aka kunna, amma in ka zo kusa, sai ka ga ashe mazaje ne suka harzuqa suka kuma fusata ba don komai ba, sai don su kammala wannan aiki da zai kawo ci gaban Arewa cikin xan qaramin lokaci.

Za ka gan su rukuni-rukuni, waxansu sun yi gumi sharkaf, suna hutawa domin waxansu rukunin sun karve su. Kusa da ma'aikatan kuma ga makaxa da mawaqa nan na sosa wa mazaje inda yake yi masu qaiqayi. Nan kuma ga zabiyoyi na yi wa mazaje qaimi. Nesa da ma'aikatan sai hayaqi ke tashi domin mata madafa abinci

---

1 Hira da Malam Tanimu Zariya ran 10 ga Satumba 1984

2 AR2/NNR/1910-11

3 *Ibid*., ran 21/12/84

sun duqufa wajen rangaxa wa ma'aikata miya. In kuma ka lura sosai sai ka ga Turawa Injiniyoyin aiki na kaiwa da komowa, babu abin da suke yi sai ba da umarni. Har ma waxansu kuma sun buxe baki suna masu al'ajabin waxannan ma'aikata, suna kallon yadda mazaje ke nuna nagarta.

An fara aiki gadan-gadan a shekarar 1909, a cikin watan Maris na wannan shekarar, an fara da leburori xari uku (300) a hankali ana samun qarin ma'aikata, a qarshen shekara an sami yawan leburori da ya kai dubu uku da xari xaya da casa'in da xaya (3,191). Aikin saran-qasa wato *Earthwork* da aka faro daga Kudu da kogin Kaduna, har an sami kammala shi. Yana da tsawon mil ashirin da biyu da rabi (22½ miles).

Haka kuma aikin da aka datso daga Zariya a watan Yuli na shekarar 1909 aka nufo da shi kogin Kaduna; an fara da leburori xari huxu da saba'ini (470) shi ma kafin qarshen shekara sun kai yawan dubu huxu da xari xaya (4,100).

An sami kammala aikin mil ashirin da takwas (28 miles) da aka shata. Saboda haka a cikin watanni tara da fara wannan aiki, an sami yin aiki mai tsawon mil hamsin da rabi (50 ½ miles). Yawan leburori sun kai dubu bakwai da xari buyi da casa'in da xaya. (7,291).

An raba aikin kashi biyu: yankin kudanci da yankin Arewaci *Northern Section da Southern Section* don a samu sauqin aiki cikin tsari mai kyau. Mista Razdan Grier da Mista A.R Browne da Mista *Kay* suke da alhakkin lura da aikin na yankin Kudu. Mista Renny Tailyour da Keftin Buruside na ma'aikatar Relwe, suke lura da aiki na yankin Arewa.[1] Duk waxannan shugabanni sun yi aiki wurjajan wajen ganin aiki ya tafi sosai ba tare da wata matsala ba.

Haba! Malam ai ko injinan zamani sa rufa masu asiri, don kuwa sun laqwame wannan gawurtaccen aikin kadarkon cikin watanni biyar kacal. Turawa sun yi mamakin gama wannan aiki, don haka muqaddashin daraktan Reluwe, Mista G.M. Bland ya aika wa da Gwamna labarin wannan mashahurin aiki, ya ce da shi "Ba a tava gama irin wannan aiki cikin xan qaramin lokaci ba a duk Nahiyar Afirka kamar a wannan lokaci. " Mista M. Bland ya ce da Gwamna Lugga, "Wannan abin mamaki ne a gama wannan gada cikin watanni biyar! "

Wannan gada na da daki iri uku: akwai masu tsawon qafa xari (100 feet) da guda biyu masu tsawon qafa hamsin da biyar (55 feet) da biyu masu tsawon qafa arba'in (40 feet) da kuma xaya mai tsawon qafa talatin (30 feet). An gama aikinta a cikin watanni biyar. Ta na da kwata ta daven siminti da su ka kai bisa ko tsawon kafa talatin (30 feet).[2] An kuma wahala wajen kafa harsashinta. A shekarar 1911 aka buxe wannan gada.

---

[1] *Provincial Gazetteer* shafi na 31

[2] *Provincial Gazetteer* shafi na 19

Ita wannan gadar jirgin, an kashe zunzurutun kuxi har wajen fam dubu bakwai da xari bakwai da sittin da biyar (7,765), an kuma buxe ta a cikin watan Mayu na shekarar 1911. An xauki lokaci mai tsawo mutane da motoci suna amfani da wannan gada 'mahadi-ka-buge'. Idan jirgi zai wuce, sai a rufe hanyar mota da jama'a, sai ya wuce sa'an nan jama'a su ci gaba da zirga-zirga a kan wannan hanya. Haka aka riqa yi har wajen misalin shekaru *arba'in* da huxu (46). A cikin watan Agusta na shekarar 1957 ne aka buxe hanyar gadar motar da aka gina a kan kuxi fam dubu xari da ashirin da biyar (£125,000).

Jin kaxan da gama aikin kadarkon jirgi sai aikin diga ya tafi cikin hanzari kuma bisa tsari. Saboda qarin leburori da aka samu kammala, sauran aikin ya sauqaqa qwarai, domin leburori sun himmatu, suna yin aiki mai nisan mil ashirin da biyar zuwa arba'in na tsawon hanyar a kowane wata. Domin himmatuwar waxannan bayin Allah, 'yan sare itatuwa da sassabe sagagin bisa hanyar da aka yi safiyo, sun kammala aikinsu cikin watan Yuni na shekarar 1910, wato har sun kai Kano. Yan jera sikwati da xora qarfen dogo su masun ci qarfin aikin sosai, har sun kawo garin Rigacikun a ranar 22 ga watan Disamba na shekarar 1910. A wannan gari ne aka yi 'yar qaramar hanyar jirgi wadda ta kai Bauci domin kwaso ma'adinai.

Leburorin aikin jirgin Baro zuwa Kano, sun qara yin bajintar da ba a tava yin irinta ba a duk nahiyar Afirka a wannan lokacin, wato wajen aikin *Plate laying*, jera sikwati da xora qarfen dogo, sun yi aiki mai nisan mil 6l/2 a rana guda. Wannan aiki da aka yi a gaban garin Rigacukun ya bai wa muqaddashin daraktan Reluwe, Mista G.M. Bland mamaki. Wannan abin bajintar da suka yi in ji Mista Bland, ya faru ne saboda qwarewar Turawan aiki, nagartar leburori da samun isasshen goyon bayan Sarakuna.

Leburori da ma'aikata sun cika umarni, sun kai hanyar jirgi Zariya cikin watan Janairu, sun kai Kano kuma a cikin watan Maris duka cikin shekarar 1911. A kusan qarshen shekarar kammala wannan aiki, an sami leburorin aiki masu ximbin yawa:

31 ga Maris	— 8,804
30 ga Yuni	— 6,000
30 ga Satumba	— 7,000
31 ga Disamba	— 9,000 [1]

Waxannan jimillar leburori, ya qunshi ayyukan Baro zuwa Kano da kuma 'yar qaramar hanyar jirgi zuwa Bauci. Wannan aiki da aka faro shi ranar 8 ga watan Agusta na shekarar 1907, an kammala shi a ranar 28 ga watan Maris, na shekarar

[1] *Annual Colonial Reports* – 1911, XVII; Means of Communication: Road Transport.

1911. An samu shekaru uku da watanni takwas cif-cif bisa wannan aiki. An kashe kuxi don wannan aiki har fam miliyan biyu da dubu xari huxu da casa'in da shida da xari biyu da talatin da huxu. (2,496,234).

Gama wannan aikin ya sa Sarakuna da shugabanni da sauran jama'ar Arewa murna da farin ciki, domin sun hangi wannan abu zai bunqasa qasashensu da arziqin jama'arsu.

Jirgin qasa ya fara zuwa Birnin Zazzau a ranar 20 ga watan Janairu na shekarar 1911. An buxe hanyar jirgin cikin watan Fabrairu na wannan shekarar. Wanda ya buxe muhimmiyar hanyar shi ne Muqaddashin Gwamna, Mista C.L. Temple. A wannan lokaci Zage-zagi sun nuna farin ciki qwarai da gaske, farin cikin samun nasarar aikin hanyar jirgin, kuma suna murna da zuwan jirgin qasa birninsu. Domin su nuna farin cikinsu, sai aka yi babban bikin zuwan jirgi na farko birninsu. Cikin xan qaramin lokaci sai Sarki da manyan shugabanni suka shiga shirye-shiryen bikin Daba, an gayyato baqi daga ko'ina cikin qasashen Hausa. A wannan biki ne qabilun da ke kudancin Zariya suka fara shiga Birnin Zazzau. Domin su ma an gayyato su zuwa wannan biki.

An yi wannan bikin Daba a ranar 22 ga watan Yuni na shekarar 1911. Lokacin wannan biki, an kawo jiragen qasa na musamman guda ashirin. Manyan baqi da shugabanni sun hallara. Ga 'yan Sanda, ga sojoji masu fareti da sojojin doki xauke da bindigogi duk sun haxu ga 'yan Begila da Badujala ga Makaxa da Mawaqa da sauran jama'ar gari da manyan baqi, kowa sai murna yake yi. Wanda ya buxe bikin Dabar shi ne, Muqaddashin Gwamna Mista C.L. Temple.[1]

Taragan jiragen sun cika maqil da 'yan biki, sun bar Zariya da safe misalin qarfe 7.00 na ranar 2 ga watan Yuli na shekarar 1911. Jirgi ya taho da su, ya biyo ta Kaduna sai Minna zuwa Dungurun zuwa Baro. Ba su isa Lakwaja ba sai ranar 3 ga watan Yuli na shekarar 1911, wato kashegari. An yi wannan muhimmiyar tafiyar tarihi wato hawan bangirma na musamman cikin sa'o'i talatin.[2] A cikin waxannan sa'o'i (30hrs) 'yan bikin 'Dabar' na cike da farin ciki da murna da jin daxi. A lokacin da ake shagalin wannan biki kuwa Kanawa na shirye-shiryen yin nasu qasaitaccen bikin zuwan jirgi qasarsu.

Jirgin ya fara shiga birnin Kano a ranar 28 ga watan Maris na shekarar 1911. A wannan ranar dai Kanawa sun nuna murnarsu da kuma farin cikin samun nasarar aikin hanyar. Saboda wannan muhimmiyar ranar ce a cikin tarihin birnin Kano, Sarkin Kano Abbas ya gayyato maqwabcinsa, Sarkin Katsina Muhammadu Dikko da ya zo Kano, ya halarci bikin farkon zuwan jirgin qasa birninsa.

---

[1] *Provincial Gazetteer*, shafi na 32.

[2] Annual Colonial Reports – 1911, *XVII; Means of Communication*: Road Transport

Sarkin Katsina Muhammadu Dikko, ya yi na'am da wannan gayyata, ya kuma taho tare da jama'arsa cike da farin ciki. Birnin Kano a wannan rana maqil yake da baqi da 'yan gari kowa sai murna yake yi.

Kashe gari wato ranar 29 ga watan Maris na shekarar 1911, Sarkin Kano tare da babban baqonsa Sarkin Katsina da sauran manyan baqi, an xauke su a cikin jirgin aka kuma yawata da su zuwa kogin Calawa domin girmamawa, tafiya mai nisan mil 12. An yi wannan 'Hawan' ban girma cikin farin ciki. Sarkin Kano ya qara jaddada goyon bayansa ga wannan aiki, ya kuma yi qoqarin qarin leburori.[1]

Bikin daba na baiwa Turawan Mulki sha'awa sosai har masun shaqu da shi. An yi masu Daba a Dungurun kafin a fara aikin jirgi. An yi qasaitattun bukukuwan daba a Zariya da Kano. An gama waxannan bukukuwa ke nan, sai Gwamana Lugga ya ce a yi dabar sarkuna a birnin Kano. An yi qasaitaccen bikin daban a qarshen shekarar 1912, a cikin watan Disamba.[2] Sarakunan qasashen Hausa da shugabannin sun halarci wannan daba. A na jin daga dabar da Muqaddashin Gwamna C.L Temple ya haxa a Zariya, a shekarar da ta gabata, ai sai wannan ta Gwamna Lugga a Kano a qasaita. Amma inda wannan dabar ta bambanta, ita daba ce ta Sarakuna da shugabanni wato *Dabar of Emirs and Chiefs* . Ga alama dai Gwamna Lugga na son birnin Zariya. Bini-bini sai ya kawo mata ziyara. Kafin ya tafi dabar Sarakuna a birnin Kano, sai da ya ziyarci birnin Zazzau.

Bayan da aka kammala hanyar wannan jirgi, sai babban Baturen duban aiki ya zo daga Ingila. Shi wannan Bature mai suna Manjo *Waghon* ya kawo ziyarar duba aiki ranar 21 ga watan Oktoba na shekarar 1911. Ya duba aikin hanyar Baro zuwa Kano da kuma 'yar qaramar hanyar jirgi zuwa Bauci. Ya koma garinsu ranar 28 ga watan Nuwamba na shekarar 1911.

Amfanin Hanyar Jirgi

Kafin hanyar jirgi ta samu, jama'a na tafiye-tafiye kan jakuna da raquma da shanu, ko kuma a qasa, musamman wajen fatauci wato fatake. 'yan kayayyakin da ake yiwo fataucinsu kuwa kaxan ne, amma buxe wannan hanyar jirgi daga Baro zuwa Kano ta havaka kasuwanci da hulxa da juna tsakanin mutanen Nijeriya ta Arewa da na Kudu.

Ita wannan hanya, ita ce jigon qarfin arziqin Arewa, saboda cuxanyarsu da mutanen Kudu ta fuskar siyasa da kasuwanci. Hanyar ta taimaka wajen sashen Arewa, da haxa Kudancinta, wanda Gwamna-Janar Lugga ya yi a cikin shekarar 1914.

---

[1] Annual Colonial Reports – 1911, *XVII; Means of Communication*: Road Transport

[2] *Provincial Gazetteer*, shafi na 33.

Turawan da suka yi wannan aiki da Sarakunan da suka taimaka da leburorin da suka sha jar wuya wajen yin wannan aiki, dukkansu sun yi wa qasar nan abin arziqin da ba za a manta da su ba. Kowa ya san dai Nijeriya ta Arewa tun kafin zuwan Turawa, ta yi nisa wajen harkar kasuwanci, sa'an nan kuma Allah Ya albarkace ta da arziqin qasa da na jama'a. Amma bayanzuwan Turawa, buxe kasuwanci da sauran qasashen duniya masu nisa da ya auku, sai aka farga da cewa babu wani teku ko qasaitaccen kogin da jiragen ruwa za su riqa zirga-zirga, waxanda za su haxa ta da sauran qasashen duniya kamar garuruwan da ke bakin teku da ke sashen kudancin Nijeriya.

Amma saboda an wayi gari da makekiyar hanyar jirgin qasa shi ya sa wannan rashi bai fito fili ba, bai kuma kawo cikas ba wajen arziqin qasashen waxannan wurare. Ta hanyar jirgi ne kayayyakin mutanen Arewa kamar gyaxa da auduga da fata da sauransu za su iso bakin teku, inda za su bi teku su isa qasashen Turai. Haka kuma kayayyaki kamar na ma'aikatu da gini da magunguna da sauransu, za su iso sashen Arewa a Nijeriya daga qasashen Turai. Idan waxannan kayayyaki sun iso bakin teku a Ikko ko Fatakwal, sai a zuba su a taragunan jiragen qasa a yiwo Arewa da su. Yaya waxannan qasashen sashen Arewacin Nijeriya, misali za su kasance inda babu hanyar jirgi?

Bunqasar sashen Arewacin Nijeriya ta fannonin kasuwanci da siyasa, sun dogara ne kan wannan muhimmiyar hanyar jirgi. Cinikayya tsakanin 'yan Nijeriya da ke garuruwa daban-daban a cikin wannan qasa, ta sauqaqa matuqar gaske. Kayayyakin gine-gine da kayayyakin ayyukan hanyoyin motoci da motocin kansu, duk ta jirgi suka shigo sashen Arewacin Nijeriya. An yi shekaru masu yawa ana matuqar amfani da wannan hanya kafin hanyoyin motoci su zo.

Ma'aikatar jirgi tana samun ribar dubban Nairori a kullum saboda 'yan kasuwa da 'yan makaranta da sauran matafiyana zirga-zirga cikin jiragen qasa zuwa wurare daban-daban a cikin wannan qasa. Don haka kusan kowa ya wayi gari ya ga hanyar jirgi take ta qungurmin jeji ta ratsa qauyuka da birane, amma wataqila babu wanda ya tava tambayar bayin Allah da suka yi wannan muhimmin aiki. Wannan abu bai miskile mu ba. A taqaice dai ko da yake babu teku a sashen Arewa na Nijeriya, amma leburori sun shimfixa muhimmiyar hanyar jirgin qasa wadda take da muhimmanci, kamar yadda teku take ga sashen Kudu na Nijeriya.

Bayan kusan shekaru arba'in da kafa hanyoyin jirgin qasa a Arewa, sai arziqinta ke bunqasa cikin hanzari. Ma'aikatar Reliwai ta bada rahoton ta na shekarar 1954 wanda ya bayyana irin ci gaban da Reliwai ta samu da kuma yadda hanyoyin jirgi ke qara bunqasa arziqin Arewa cikin hanzari.

Wannan labari na game da ma'aikatar reliwai, *Mr. J. Wilkinson* ya ba da shi a wayar iskar Nijeriya kwanaki. Ya ce ma'aikatar reliwai muhimmiya ce a Jihar Arewa, tum ba ga waxanda suka ga sha'anin sufuri na qasar nan ba? Ta reliwai ne

kaxai inda a ke xaukar kayayyaki da amfanin gona daga Jihar Arewa zuwa tasoshin jirgin ruwa a Ikko ko Fatakwal. Ana ma iya kiranta ran Jihar Arewa.

A shekarar kuxi ta 1953 zuwa 1954, ma'aikatar reliwai sun xauki muhimmiyar kalman nan ta ministan Nijeriya na sufuri, inda ya ce, "Don a sa jama'a su sake amincewa da reliwai. Ministan sufurin nan, wanda yake xan Arewa ne, Mai girma Abubakar Tafawa Valewa, ya yi amfani da waxannan kallomomi a kan wani rahoton reliwai na shekarar 1953 zuwa 1954. Littafin nan yana da shafi 76, akwai hotuna wanda mai karantawa zai yi sha'awarsu. Wannan labari na game da Reliwai, Mr. J. Wilkinson ya bada shi, kamar haka:

Bari mu fara kan waxansu jimilla guda biyu, waxanda ni ke tsammani za su ba ku al'ajabi. Jimillar yawan hanyar jirgi ta reliwai a duka Nijeriya fiye da mil dubu da xari tara ne. A cikin wannan jimilla, ko ka yarda ko kada ka yarda, fiye da mil dubu da xari biyar a Jihar Arewa yake. Sai mu ce hanyar jirgi na Jihar Gabas da Yamma, idan aka tara su gaba xaya, kamar mil xari uku da hamsin ne kawai.

Tafiyar mil dubu da xari biyar, tafiya ce mai nisa, amma bari mu dubi sha'anin jirgin qasa a Jihar Arewa. Mun taso daga Offa wadda take kan iyakar lardin Ilori, mun faxa hanyar jirgi ta Ikko zuwa Jihar Arewa. Muka ratso ta garin Ilori, mu gitta shahararriyar kadarkon nan ta Jebba a bisa Kogin Kwara zuwa Zungeru, wadda a da nan ne Hedkwatar Lord Lugard.

Daga Zungeru, muhimmiyar tasha da za mu iso ita ce ta Mina, inda hanyar jirgi daga Baro ta haxu da wannan babbar hanya. Wannan hanya ta Mina zuwa Baro an daxe ana amfani da ita, misali fiye da shekara hamsin. Har yanzu kuwa tana da matuqar amfani, tum ba cikin xan lokacin nan ba cikin shekara, lokacin da jiragen ruwa na wuta suna iya isowa Baro, su xauki amfanin gona a nan. Reshen hanyar Baro da jiragen ruwa na wuta su masuna irin nasu qoqari wajen jide gyaxa daga Kano.

Ina iya tuna shekara biyu ko uku da suka wuce lokacin da Mai girma Gwamna ya sanya jirgin nan Valiant cikin aiki, don ya sauqaqe wa kayan wajen jidewa. Duka dai a kan xauki ton dubu ashirin da uku (23,000) na gyaxa daga Jihar Arewa a shekara ta hanyar Baro.

Daga Mina sai babban layin nan ya nufi Arewa zuwa Kaduna Jamsin, inda hanyar Jihar Gabas daga Fatakwal ta haxu da wannan. Sai dai bai yi daxi qwarai ba game da shirin reliwai mutum ya shigo jirgi daga Ikko zuwa Fatakwal, tilas mutum ya biyo har ta Kaduna, sa'an nan ya gangara zuwa Fatakwal. Amma idan mutum ya duba

yadda gavar kudancin Nijeriya yake, sai ya ba kansa amsar dalilin da ya sa haka. Idan aka yi hanyar jirgi a irin waxannan wurare, za a kashe kuxi masu ximbin yawa.

Daga Kaduna kuma muka nufo Zariya, nan ma wata mahaxar jirgi ce. Daga nan ne jirgi kan tashi zuwa Funtuwa, Gusau da Qauran Namoda hanyar da za ta xauke ka zuwa cikin cibiyar noman auduga da gyaxa, sa'an nan wurin samun qirgi da fatu daga wajaje Sakkwato. Idan kana so ka je Sakkwato ta wannan hanya, tilas ne ka sauka a Gusau, sa'an nan ka shiga motar bus ta reliwai. Ma'aikatar reliwai su kan yi ma'amala da motocin bas da kuma manyan lori na xaukar kayayyaki.

Mu nufi Arewa kuma, Zariya zuwa Kano, inda daga qarshe za mu kai inda aka tara himilin gyaxa, wanda mu ke jin labarinsu qwarai. Mutane da yawa suna tsammani cewa hanyar jirgi ta tsaya a Kano, amma ba haka ba ne. Ta ci gaba har kusan mil xari da hamsin zuwa Nguru ta lardin Barno. A wannan hanya ne a ke cewa akwai miqaqqiyar hanyar jirgi da a ke cewa ita ce mafi tsawo, da ba ta da kwana ko wace iri a Afirka duka. Ban sani ba ko haka gaskiya ne, sai dai na sani layin miqe yake kamar fiye da mil tamanin. Game da shaquwar qasar da na yi, zan tabbatar maka da cewa akwai zafi qwarai da gaske.

Nguru ita ce qarshen hanyar jirgi a Jihar Arewa sai kuma mu dawo Kudu mu bi layin da ya gangaro zuwa Jihar Gabas da Fatakwal. Daga Kaduna muka nufo Kafancan, mahaxar jirgi, inda za mu sami hanyar da ta fito daga Jos da ke xauko kuza da columbite daga wuraren haqo ma'adinai na Qasar Kuza. Daga Kafancan sai muka ratsa Lafiya, muka gitta Kogin Binuwai, ta bisa wani kadarko a Makurxi, hedkwatar lardin Binuwai, a biyo ta Oturkpo, sa'an nan a haye kan iyaka, a shiga Jihar Gabas.

Jirgin Bauci

Waxannan su ne hanyoyin jiragemmu a Arewa, amma dakata kaxan malam, gaskiyarka ban ambaci abokin nan namu ba, jirgin nan xam Bauci, wanda ke tafiyar mil xari da talatin da uku (133) tsakanin Zariya da Jos. Idan mutum ya ga yadda jirgin nan yake tafiya, abin sha'awa ne. Idan ma ya zo wurin hawa, sai mutum ya ga kamar zai iya sauka ya tura shi.

Dalilin da ya sa a ke kiransa xam Bauci, saboda faxin hanyar qafa biyu da inci shida ne, sauran layukan Nijeriya kuwa qafa uku da inci shida ne. Mai da hanyan nan mai faxin qafa uku da rabi yana cikin

Shirin Raya Qasa na Ma'aikatar Reliwai, wanda za a fara cikin watan Afrilu. Na sani 'yan Arewa da dama za su yi farin ciki da jin haka, don da akwai jita-jita cewa wai za a kulle hanyar nan.

Wani babban abu da ke ba da wahala a can Arewa Arewa, shi ne sama wa injin na jirgi ruwan sha. Abin sha'awa ne da aka ba da labari cewa injin jirgin nan guda goma masu aiki da baqin mai da reliwai ta yi oda, za su yi aiki a hanyar Zariya zuwa Kano kawai. Masu aiki da kwal kuwa ashirin da tara (29) a dawo da su su yi aiki a waxansu wurare. Waxannan injuna guda goma za su iya jan kayan da injin ashirin da xaya (21) masu aiki da kwal za su iya ja. Za su kuwa iso tare da qarin waxansu masu aiki da kwal kuma. Idan suka iso reliwai na iya jida dukan kayan shekarar 1955 zuwa 1956.

Mutane suna kawo suka qwarai game da jinn reliwai, tum ba gazawarsu ba wajen jide himilin gyaxar Kano. Ba gaskiya ba ne a ce reliwai ba ta yi qoqarin kyautata abin ba. Abu xaya da aka faxi cikin rahoton, shi ne jide gyaxa daga Arewa zuwa bakin ruwa, yana cikin manyan abubuwan da reliwai ta fi samun kuxi kansu. A bayyane yake cewa reliwai na fata ta zama kamfani cikin watan Afrilu na baxi.

Daga ran 1 ga Nuwamban shekarar 1953 farkon shigowar kaka, ton dubu xari da tamanin da shida (186,000) na gyaxa na kakar bara ya rage a jide. Amma a watan Afrilu na bana an rage wannan ya zama saura ton dubu shittin (60,000). A qarshen shekarar kuxi, reliwai ta jide ton dubu xari huxu da ashirin da xaya (421,000) na gyaxa. Ba a tava samun haka ba. Hukumar jirgi ta yarda ba a sami gyaxar da ta ragu na wata shekara ba, ko da an sami qaruwar gyaxa da yawa. Himilolin gyaxa na Kano ba zai zama abin kallo ba kuma.

Kada ka yi tsammanin cewa gyaxa ce kawai amfanin gonar da reliwai ke xauka, akwai auduga, goro, qirgi da fatu, kwal, katako, suminti, shar kaxan ma ke nan daga cikin abubuwan da reliwai ke samun kuxi.

Duk da waxannan hanyoyin sufuri, sai a ga faxuwa a ke. Lallai kan akwai faxuwa, don da yawa daga cikin ku, ku kan ji labarin yadda 'yan ture ke fasa wagunoni lokacin da jirgi ke tafiya, su turo kayan da ke ciki. Rahoto ya ba da labari cewa cikin shekara uku da suka wuce, am fasa wagune 40,13 da 17 bi da bi.

Na ambaci Shirin Raya Qasa na Shekara Biyar da za a fara a watan Afrilu mai zuwa. Ban da sake hanyan jirgin Bauci, sashen wajen Jos zuwa Kafancan shi ma za a sake hanyar da manyan qarafa, za a sake waxansu tasoshi da dama. Za a gama shedin injin jirgi a Mina,

Makurxi da wakashof na Zariya. Kaxan ke nan daga cikin abubuwan da za a yi.

Wannan xan bayani kaxan ke nan daga cikin rahoton ma'aikatar reliwai na shekarar 1953 zuwa 1954. Idan lallail kana sha'awa, sa'an nan naka kofen ka karanta. Na tabbatar ban da qaruwar sha'anin reliwai da za ka yi, za ka kuma qaru da tarihin Nijeriya .[1]

Dubban leburorin da suka yi wannan aiki, Ko da yake ba su more guminsu ba, amma sun sadaukar da kawunansu, sun daure sanyin kaka da qurar bazara da haxarin aiki da ciwace-ciwace da muggan namun jeji. Sun kuma duqufa sun yi wa qasarsu abin da bai kamata a manta da su ba, amma abin takaici sai ga shi an yi biris da abin da waxannan bayin Allah suka yi. Wajen Turawa kuwa, ai su buqatarsu ta biya don sun kwashi garabasar arziqin qasarmu sun tafi, sun gina biranensu da arziqin qasarmu, sannan kuma da jivin jama'armu.

Wani babban abu da aikin hanyar jirgin Baro zuwa Kano ya haifar, shi ne gina garin Kaduna wadda ta zama sabuwar hedkwatar Nijeriya ta Arewa. Dalili kuwa, shi ne tun da Gwamna Lugga ya karvi mulkin Nijeriya ta Arewa, yake ta neman wajen da zai dace da zama hedkwatarsa, amma bai samu ba.

Daga qarshe dai sai ya haqura da Dungurun. Har ma kwamitin 'yan binciko sabon wajen da zai dace da zama hedkwata, ya kafa su tun a farkon shekarar 1900. Kamar yadda aka yi bayani, Manjo Morland da qungiyarsa su aka umarta da su bi tsawon kogin Kaduna su gani, ko za su sami wani wuri mafi dacewa.

Rashin gano wannan waje da aka kafa Kaduna, ba sakaci ne Manjo Morland da qungiyarsa suka nuna ba, a'a, abu ne mawuyaci a ce mutum ya bi cikin kogi yana tafiya yana kuma lura da gavar kogin, domin in ba a yi sa'ar gaske ba, ba yadda za a yi ya dace ya dubo gavar kogin da za ta dace da kafa hedkwata. Ballantana in aka yi la'akari da cewa, shi Manjo Morland an ba shi qurarren lokaci, saboda waxannan dalilai, sai ya zamana Baturen bai gano wannan wuri ba tun farko.

Aikin wannan hanyar ya taimaka qwarai da gaske, wajen gano wajen da aka kafa garin Kaduna. Na farko dai Turawan sun sami tsawon watanni biyar suna aikin gadar jirgi. Wannan dama da suka samu sun bazama cikin wannan jejin da ke Gabas da kogin. Zamansu a wannan waje ya karantar da su yadda yanayin wajen yake sosai da sosai. Dalili na biyu kuma, shi ne hanyar jirgin da ta keta jejin, wannan ai ba qaramar dama ba ce Turawan suka samu wajen duba wurare. Zirga-zirgar jirgin qasa tsakanin Baro zuwa Kano a cikin shekarar 1911-12 sun qara wa Turawa sha'awar kafa garin Kaduna.

---

[1] GTK, 1 ga Disamba 1954

Turawa shugabanni da ma'aikata sun daxe suna qorafi da zaman garin Dungurun, amma dawowar Gwamna Lugga daga qasar Hong Kong, sai waxannan koke-koke suka yi tasiri sosai, a shekarar 1913. Don an zartar da hukuncin da a hanzarta tashi daga wannan gari zuwa Kaduna. Gidan Kwalba wato *Prison Yard*, wanda Gwamna Lugga ya ce a mayar da shi Gidan Tavavvu, hakan bai yiwuwa. Soboda Gwamna H. Clifford, wanda ya gaji Lugga cewa ya yi wajen bai dace da zama gidan Mahaukata ba. Sir Clifford shi ya assassa tasowa daga Dungurun, don haka sai aka kwashe abubuwa masu amfani, aka bar sauran suka lalace.[1]

Dajin wannan waje, (jejin da ke Gabas da hanyar jirgin, kuma Arewa da gadar jirgin kogin Kaduna), ya sa Turawa gode wa Allah, domin abin da suke nema shekara da shekaru ga shi Allah Ya nuna masu, wato wajen da ya fi ko'ina dacewa da kafa hedkwata. Amma kafin a ci gaba da wannan labari sai a yi bayani akan yadda aka yi fafitikar neman sabuwar hedkwata.

Neman Sabuwar Hedkwata

Ko da yake Gwamna Lugga shi ne ya zavi Dungurun ta zama hedkwata, amma ba a ta gamsar da shi ba ne, domin ba a sami wani waje da ya fi ta dacewa ba, domin zaman Turawa a Dungurun suna yi ne a gwaggwafe. Saboda haka suna ta Allah-Allah su sami waje mafi dacewa.

Zaman Dungurun ba shi da daxi ko kaxan, yanayin garin ya cika zafi, ga rashin armashi. Dungurun kuma Allah Ya yi ta da bala'in sauro da qazanta mai tayar da hankali. Saboda waxannan dalilai, babban Kwamishinan wannan lokaci, Sir E.P.C. Girouard a shekarar (1901-1908), ya yi Allah-wadai da zaman wannan gari. Ya ce ko kaxan wannan gari bai cancanta da zama ba, balle fa matsayin hedkwata.

Sarkin Kano Abbas ya tava sauka da ayarinsa na jama'a da dawakai. Saukarsa ke da wuya sai ya buqaci a nemo masa dammunan hatsi guda xari, domin a ciyar da dawakai. Amma abin takaici da qyar aka samo dami uku. Shi da kansa ya yi Allah-wadai da wannan garin, ya ce kar Allah Ya dawo da mu wannan waje. Allah kuwa Ya karvi roqon Sarkin, don kuwa 'yan shekaru kaxan, sai ga shi an gano Kaduna, inda aka mayar da hedkwata. Domin cimma wannan buri sai aka hanzarta samo waje mafi da cewa.

An kashe maqudan kuxi wajen tasowa daga Jebba zuwa Dungurun, an kuma kashe su wajen gine-ginen mahalli da ma'aikatu, dalilin haka ya tilasta zama a wannan gari a dafe-dafe har sai inda hali ya yi. A wata amsar takarda da Gwamna Lugga ya aikawa da Mista Chamberlain daga Kano a shekarar 1903, ya ce:

---

[1] Dantsoho Mohammed, *Zungeru*, shafi na 96.

An riga an kashe maqudan kuxi saboda hanqoron yin ayyuka, an kashe kuxaxe masu yawa. Dalilin haka ya sa nake ganin maganar sake tashi zuwa wani waje ba zai ta so ba sai an samu shekaru nan gaba. Mun gina gidajen Turawa 28, da babban asibiti, da wajen shaqatawan sojoji "Officers Mess, " da babbar kotu, da gidan Gwamna... Ana yin kadarkai akan rafukan Dogo da barikin sojoji. Haka kuma an yi xakunanan ajiyar kaya, "storehouses, " da gidan 'yantattatun Bayi, da gidajen akawuna, da xakunan dawakai. An zavi wannan waje ne ta fuskar siyasa, duk kuma baqin da suka zo su na yabawa yin haka. Ba zan tuna da wani wanda ya kawo bambancin ra'ayi ba. Waje ne kuma mai lafiya bayanin da na samu daga masu kula da lafiya, sun nuna cewa an kwantar da mutum bakwai a asibiti a Lakwaja, amma ba a kwantar da kowa ba a Dungurun.[1]

Babu shakka abin takaici ne rashin samun wurin zama mafi dacewa, a lokacin da ake buqatar samunsa da mutuqar gaske. Musamman idan aka yi la'akari da kuxaxen da ake kashewa wajen tashi daga wani gari zuwa wani gari, kamar yadda aka taso daga Lakwaja zuwa garin Jebba daga nan kuma sai a taso zuwa Dungurun. To, idan aka tashi daga nan, ina za a nufa? A cikin wannan hali ne Gwamna Lugga ya bar Nijeriya a 1906, zuwa qasar Hong Kong inda ya riqe muqamin Gwamna.

Kamar yadda aka yi bayani, Babban kwamishina Sir Percy Girouard wanda ya gaji Gwamna Lugga bai voye qyamarsa ga wannan hedkwatar ba. Shi ne ya fito fili ya yi Allah wadai da wannan hedkwatar, ya kira ta, wofintacciyar hedkwata ga kowa *universally condemned as a capital*, da zamansa a kan karagar mulkin Arewa. Amma duk da haka ya zauna a gwaggwafe a cikinta har tsawon shekara guda, inda ya qara su kan wannan gari da cewa: "Duk da matakan da aka xauka wajen kawar da sunqurun wannan gari amma duk sun ci tura. Yanayin garin Dungurun ba shi da daxi ko kaxan ya kan sa mutum yin jagalam.[2]

Turawan mulki sai suka tsinci kansu a tsaka mai wuya, a zauna babu daxi babu kuma wurin zuwa da ya dace. Wannan shi ne halin qaqa ni kayi! Wannan matsayi sai ya zama abun kunya ga gwamnati da Ofishin Mulki. An kai halin da duk rahoton da zai fito daga wannan yanki, sai ya aiko da kukan neman a ceto mazauna wannan gari daga cunKwason jama'a da tavarvArewar mahalli. Amma kuma ba wanda zai yarda a sake fidda maqudan kuxi wajen kafa wata sabuwar hedkwata, don kuwa an yi an gani ba a ji daxi ba. Har yanzu ma cizon yatsa ake yi akan dukiyar da aka varnata a garin Lakwaja da garin Jebba. Hasali ma idan aka

---

1 *Nigerian Handbook*, Vol. 9, shafi na 256.

2 *Ibid*. shafi na . 256-257

bar Dungurun babu wajen zuwa. Irin wannan hali, ya sa Turawan Mulki kamar su sa hannu a kansu su varke da kuka don takaici.

A cikin wannan hali mara daxi, sai aka riqa tunanin ko Kano za a koma ne. Kano gari ne tumbin giwa wanda ya shahara a Nijeriya ta Arewa. Amma abin da ya yi wa wannan batu da ya taso karan-tsaye, shi ne babbar maganar nan muhimmiya ta bin tsarin kafa hedkwata a waje wanda ba shi da alaqa da wata qabila, ko kuma wani gari, kamar hedkwatocin qasashen *Canada*, da *Australia* da Afirka ta Kudu. Ya zan tilas a sami hedkwata wadda ba za ta haifar da qorafi ko kishi da qyashin wata qabila kamar *Montreal ko Quebec* ta *Canada*, da *Melbourne* ko *Sydney* da *Johannesburg* ko *Cape Town* ta Afirka ta Kudu.[1] Ka ga ke nan idan aka kafa hedkwata a birnin Kano, Kanawa za su zo daga baya suna qoqarin karvar garinsu. Wannan zai vata shirin Turawan mulki wajen kafa hedkwata.

A na cikin haka ne, sai aka ce ga wajen Bauci-Filato mai yanayi mai kyau da armashi, aikuwa wannan waje ba shi da na biyu wajen dacewa da a mai da hedkwatar Arewa. Shi kansa Gwamna ya yaba wa yanayin wannan wuri, ya kuma yi tunanin gina gidan tavavvu wato *Sanatorium* a wannan waje, har ma ya tuntuvi Sakataren Mulki da wannan batun, inda ya ce da shi idan har an tashi daga Dungurun ya zama wajibi, to cikin Arewa za a dosa ko Arewa Maso-Gabas wajejen manyan tsaunuka inda za a kai hanyar jirgi.[2]

Shawarwari da aka tsayar a kanta ta haxa Arewaci da Kudancin Nijeriya da aka cimma a shekarar 1912 zuwa 1914, da kuma qara naxa Sir Frederick Lugard a matsayin gwamnan waxannan yankuna, ya ba da wata damar tada Dungurun ba tare da yin hakan ya kawo wani qorafi kan kashe kuxi ba. A wannan muqami na Gwamna Lugga shi ke da iko da Haxaxxiyar qasa da kuma ikon zartar da hukuncin kisa.[3] Saboda samun wannan sarari ne ya sa, gwamnan ya fito fili yana sukar wannan hedkwata, yana cewa a rahotonsa: "Dungurun ta gama amfani, saboda ta cika matsanancin zafi da yawan sauro. "[4] Haka kuma gidajen katako samfurin Lugga da aka kafa a garin duk sun tsufa, suna son a sake sabbi, har ma Jami'in kula da Tsabta ya yi tur da su, ya ce a cike suke da qwari da jemagu, har wannan abun ya zama abin qyama. Don haka ne ya bada umarnin ko a sake sabbin gidajen ko kuma a koma ga xakunan qasa cikin hanzari. Ana cikin wannan mawuyacin hali ne sai aka yi gamo-da-katar.

---

1 *Nigerian Handbook* shafi na 257

2 *Ibid*.

3 *Ibid*.

4 *Ibid*.

.

An ce, "mai nema yana tare da samu ." An samu kusan shekaru goma ana neman waje mafi dacewa da kafa sabuwar hedkwatar Arewa. An sha kuma wahalhalu iri-iri, har Allah Ya sa aka yi katari da samun wuri mafi dacewa. Bayan wuya sai daxi, ga sabon waje an samu kamar tsuntsu daga sama gasasshe. Ga abin da Kirk-Green da Campbell wasu masana tarihi suka rubuta game da wannan katarin:

> *Gwamna Lugga ya yaba wa wannan sabon wuri da aka samu, a dai-dai wajen da hanyar jirgi ta kai tudu mai tsawon qafa 2,000, a kuma wajen da ya qetare kogin Kaduna, kuma misalin mil xari biyar da saba'in (570) daga Ikko. Yanayin wajen mai kyau ne yana da sanya annashuwa, qasar wajen ita ma tana da qyau da albarka ta kuma dace da ciyayi da fulawoyi. Akwai ruwa mai kyau kuma isasshe. Wannan waje yana mil hamsin (50) tsakaninsa da Zariya cibiyar kasuwanci. Babban Jami'in Tsabta, qwararre wanda ya kuma goge wajen harkar tsabta, shi ma sai ya zama mai zakwaxin son wannan waje da ya zama sabon hedkwata.*[1]

Wannan sabon waje shi ne gavar kogin Kaduna, inda aka kafa garin Kaduna sabuwar hedkwata. Wani abin sha'awa da Turawan Mulki suka nuna wajen neman wajen da za a kafa hedkwata, shi ne haquri da hangen nesa. Duk da wahalhalu da zaman qunci da suka sha, amma duk da haka sun qi tashin wani gari ko kuma kusantar wani gari domin kaucewa rikice-rikice da ka iya tasowa idan garin ya kafu ya kuma bunqasa. Don haka ne sai suka bi da al'amarin a sannu da hankali har suka kai ga nasara.

Shirin mai da Kaduna hedkwatar Nijeriya ta Arewa, sai ya zama wani vangaren shirin haxa Arewa ci da Kudancin Nijeriya na shekarar 1912 zuwa 1914. Barkewar Yaqin Duniya na xaya ne ya kawo jinn hanzarta wannan shiri da kuma farmakin da aka riqa samu daga qasar Kamaru. Amma saboda zaman qunci da matsuwa da Turawan Mulki ke yi a Dungurun sun tilasta ci gaba da shirin gina gidaje a wannan sabon gari Kaduna, da kuma shirin tarewa wannan sabuwar hedkwata a shekarar 1916. Gine-ginen gidajen da aka yi a wannan sabuwar hedkwata masu kyau ne da kuma qarko, su na kuma da wuraren jin xumi da garwashin wuta da za a yi amfani da su a lokutan xari da hunturu. Saboda haka sai aka aika rahoton 'yan kwamitin binciko sabuwar hedkwata cikin gaggawa.

Sakataren Mulki ya amince da rahotan 'yan kwamiti cikin hanzari. Amman ba gine-gine ne abubuwan lura ba; a'a hikima da ilimi da Turawan Mulki suka nuna wajen gina gari a dajin Allah inda babu wani gari balle a ce an tayar da shi. Wato

---

[1] *Nigerian Handbook*., shafi na 258

dai Turawa ba su yarda sun yi kitso da qwarqwata ba. Babu shakka amfanin wannan hangen nesa ya yi tasiri sosai a wannan lokaci. Domin haka ne mashahuran masana tarihi *A.H.M Kirk-Green* da *M.J Campbell*, suka jaddada abin da aka yi ta nanata wa, da suka ce: *"An kafa Kaduna a dajin Allah wato "virgin bush. " Wannan ya sa a lokacin da Sir Hugh Clifford zai buxe wani bikin nuna shuke-shuke, ya misalta garin Kaduna da rami a cikin daji wato "a hole in the bush. "*[1]

Abin da suke nufi da *virgin bush* shi ne budurwar waje inda babu gari ko qauye. Wannan kuma gari yana xan cikin kwari ne a kusa da gadar kogin Kaduna, don haka ne Sir Clifford ya yi amfani da asalin wannan waje ya misalta Kaduna da wani rami ko kwari a cikin Dajin Doka. Shi ma K.J. Bryant, Baturen da ya kai ga mataimakin Di'o a lardin Zazzau ya faxi cewa wajen da aka kafa Kaduna ba shi da nasaba da wata qabila wato *Kaduna has no tribal Affliation*, domin an kafa garin a dajin doka. Saboda haka ba bu wani tarihi da za a qirqiro daga baya da zai yi iqirarin an ta da gari ko qauyen wata qabila, don kuwa ai gaskiya sunanta gaskiya.

Gaskiya Sunanta Gaskiya

Muka qetare Kogin Koriga kusa da inda shi ne hedkwatar gwamnati a yanzu a Kaduna. A lokacin nan babu gidaje, sai dai akwai yan zakoki kaxan – E. P. Miller.[2]

Alhaji (Dr) Abubakar Imam qasaitaccen Editan jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo ya ce. "In zaka faxi, faxi gaskiya komai taka ja maka ka biya. " Akwai abin da yake hudo kai a hankali da niyyar ya canja tarihi, zai iya kuma kawo ruxami ga mazauna wannan gari a nan gaba. Domin gudun kada a yi kitso da qwarqwata, ya kamata a bayyanashi tun kafin ya haddasa fitina. Wannan abu shi ne qirqiro wani gari da aka tayar wajen kafa garin Kaduna domin a amsa tambayar da ake yi kullum, wane gari aka tayar wajen kafa Kaduna?

Kamar yadda ake son canja tarihi wajen yadda aka raxa wa garin suna, haka ake qoqarin qirqiro wani tarihi da zai nuna qabilar da aka ce an kora wajen kafa garin Kaduna. Sai a dubi tarihi da idon basira da hankali da shari'a amma ba da na son kai, qabilanci ko na siyasa ba.

An yi qorafi a kan amfani da kalmar da Turawan Mulki ke faxa a bayaninsu a kan qasar da suka kafa wannan gari da qasa cewadda babu kowa a cikinta wato "no man's land " don haka ne suke kiranta Budurwar Qasa wato *Virgin Land*, da

---

1 *Nigerian Handbook* shafi na 259

2 GTK, 10/3/1954, shafi na . 6

waxannan kalmomi *no man's land* da *Virgin Land* suke yawan rubutawa a wajen ba da tarihi. An ce suna yin haka ne domin su kafa hujjar Mulkin Mallaka da qwace qasa da ke mallakar jama'a. Alal misali, cewa aka yi Turawan Ingilishi sun yi kuskure da suka qirqiro cewa qasar da aka kafa Kaduna, *Virgin Land* ce. Wannan ba gaskiya ba ne saboda kamar yadda ake cewa ne wai qabilar Gbagyi na zaune a wannan yanki tun wajen qarni na goma sha-huxu (14th Century AD). Cewa suka yi wai an kori Gbagyi daga Kaduna, aka kuma tarwatsa su suka yi Kudu kafin zuwan Turawa, a qarqashin mulkin Zazzau, wannan korar ta tsananta a zuwan Turawa Kaduna a shekarar 1900. Qasar da ba a amfani da ita an maidata qasar gwamnati. Haka kuma an yi amfani da kalmar *Virgin Land* domin kafa hujjar qwace ta ne don mallakar ta.[1]

Duk waxannan qorafe-qorafe ba su da qarfi saboda ra'ayi ne na mai rubutu a kan abin da yake zato ya faru, ko kuma yake son ya faru. Amma babu qashin gaskiya da cewa Turawan Mulki na amfani da kalmar *Virgin Land* domin mallakar qasa. Haka kuma babu qashin gaskiya wajen zargin da aka yi masu da cewa sun tarwatsa qabilar Gbagyi a qoqarinsu na kafa garin Kaduna. Ko da yake an kawo waxannan qorafe-qorafe, amma kowa ya san hujjar da Turawa suka bayar wajen mallakar qasa a Arewa bayan sun angije Daular Usumaniyya a shekarar 1903.

A wannan lokaci Gwamna Lugga ya bayyana wa Sarakunan Arewa da cewa ya karvi mallakar qasarsu. Dalilin wannan iko da Turawan Mulki suka samu, ba sai sun yi qazafin waje *Virgin Land* ne kafin su mallake shi ba. Qasar Arewa ta Turawan Mulki ne wadda suka qwata da qarfin soja. Saboda haka a jawabin Gwamna Lugga ga jama'ar Sakkwato, ya ce: "gwamnati, nan gaba, ita ce da qasar duk da Fulani suka karva bayan sun ci qasar nan da yaqi. Idan kuwa gwamnati na buqatar wani fili don wani aiki za ta amsa. "[2]

Max Lock wani babban kamfanin Turawan Ingila da ya yi nazari da safiyon Kaduna ya yi bayani sosai akan hujjojin da Turawan Mulki suka bayar wajen iko da mallakar qasa a Arewa, kamar yadda aka yi bayani.[3] Haka kuma babu qashin gaskiya wajen iqirarin cewa Turawa sun tarwatsa qabilar Gbagyi a wannan waje. A halin gaskiya babu wata qabila a dajin doka da ke Arewa da kogin Kaduna.

Hasalima dai, shugabannin Gbagyi da ke Cikun ba su barin wata qabilar Gbagyi da ke wani wajen zuwa Arewacin kogin. Haka wannan waje yake a *Virgin Land*, a lokacin zuwan Turawa. Akwai hujja da ke nuna Gbagyin Cikun na korar baqin Gbagyi da suke son zama a wannan waje har bayan shekara arba'in da

---

1 E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na .174-175

2 Max Lock Patners, *Kaduna 1917, 1967, 2017, Faber and Faber Limited London* (1967), shafi na . 82-83.

3 *Ibid*., shafi na .174-175

zuwan Nasara. A watan Disambar shekarar 1940, Sarkin Zazzau Jafaru ya yi rangadin qauyen Cikun, inda ya tattauna da Hakiminta. A wannan rangadi ne ya sami labarin cewa: "Akwai wasu mutane qabilar Gbagyi waxanda suka yo qaura zuwa Igabi, amma sai Gbagyin Cikun su ka kore su. Dalilin haka ne Sarkin ya tattauna da shugabannin Gbagyin Cikun domin ya shirya tsakanin su. "[1] Idan za a riqar korar baqin Gbagyi domin ka da su yi qaura zuwa wannan waje babu yadda wajen zai cika da waxannan qabila a qauyukan wannan yanki. A wannan rangadi sai da Sarkin Zazzau ya ce: "Na duba fayil xin kotun Gargajiyan Gbagyin da ke wannan waje, amma ban ga sunan Sarkin Kakuri ba, duk da cewa yana cikin manyan shugabanni. Na gyara wannan kuskuren cikin hanzari. "[2] Saboda dalilai masu damasun taimaka wajen maida wannan waje Buduwar Qasa har na tsawon lokaci kafin zuwan Nasara.

Budurwar Qasa

Zazzau masomar Gbagyi. Babu wanda zai raba Zazzau da qabilar Gbagyi, don kuwa tun ran gini, tun ran zane. Amma ba qabilar Gbagyi ce kawai a lardin Zazzau ba. Allah Ya azurta wannan lardi da qabilu iri-iri, masu kuma yawan gaske. Ko da yake ba yawa wannan qabila ta fi sauran qabilu ba, amma saboda qwazonta da son zaman lafiya da kowa tare da riqon gaskiya da amana, sun bata daraja babba. Domin haka ne wannan qabilar ta samu karvuwa sosai a wannan lardi, ta kuma samu amsuwa ga sauran qabilu manya da qanana.

Domin haka ne ma, Ko da yake qabilar ba ta da yawa sosai, amma ta bazu kusan ko'ina a kudanci da wasu wurare a Arewacin kogin Kaduna. Wannan qabila ta gina garuruwa da qauyuka ba ma a lardin Zazzau kawai ba, a larduna da dama a Arewacin Nijeriya musamman a yankin Neja. Mutane ne da suka yi suna wajen noma, suka kuma yi ficewajen son zaman lafiya da kowace qabila. Allah Ya yi su, ba masu son ta da hargitsi da fitina bane, ba su kuma da qyamar kowace qabila. Saboda haka sun watsu sosai ta auratayya da sauran qabilun da ke lardin Zazzau manya da qanana.

Koda suka shigo lardin Zazzau daga lardin Barno sun kafa garuruwa masu yawa, akwai kuma garuruwan da suka kafa a gavar kogin Kaduna a Arewaci da kudanci wanann kogi, tun kafin zuwan Turawa. Shi wannan kogi ya yi suna wajen yawan kadoji da ke cikinsa. Don haka jama'a ke masa laqabi da "Kogin Kaduna " wato *River of Crocodiles*. Saboda haka tsallake kogin zuwa garin Maqera ko garin Barnawa wato zuwa kudancin kogin, abu ne mai haxarin gaske. Mutane matafiya masu yawa sun halaka a cikinsa saboda da mutum ya faxa cikinsa, to, ya zama nama ke nan ga kadoji.

---

[1] Usman Xalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isyaku: The Great Emir of Zazzau*, shafi na 293.

[2] *Ibid*.

Koda Turawa suka zo, wannan yanki, abin da suka tarar ke nan. Wannan kogi da ya taso daga duwatsun Filato, yana da tsawon mil xari uku da tamanin (380 miles), ya haxu da kogin Kwara a lardin Neja. A kuma yankin da ke maqwabtaka da garin Barnawa da Maqera da Kakuri da Kinkinau, yana da manyan kadoji masu yawa. Domin haka ne sai Turawa suka sama sabuwar hedkwata garin "Kaduna. " Kamar yadda suka sa wa qasar mallakar su suna "Nigeria " daga kogin *River Niger*, wanda aka fi sani da kogin Kwara. Sai yankin wannan kogi ya zama *Niger Area*, kalmar da ta haifar da sunan Nijeriyake nan. Don haka ne wasu marubuta S. Bello, da E. Oyedele suka ce: "Kamar yadda Nijeriya ta samu sunanta daga kogin Neja, haka Kaduna ta samu sunanta daga kogin Kaduna. Ta samu wannan suna ne daga kalmar "Kaduna " wato "Crocodiles " waxanda ake samu da yawa a wannan kogi. Kamar garin *Port Harcourt* da Jos, garin Kaduna Turawan Mulki ne suka kafa shi.[1]

Ammasu qabilar Gbagyi mazauna wannan yanki, ba Kaduna (crocodiles) suka gani a wannan kogi ba. Abin da suka gani su ne koxuna wato *snails*. Domin haka sai suke kiran kogin da "Kadundna, " kalmar Gbagyi da ke nufin mu "tsallaka kogin koxuna. "[2] Wannan bayani bashi da tushe a tarihi, Turawa sai suka yi amfani da abin da suka gani na zahiri "Kaduna " suka kuma sanyawa garin suna "Kaduna. " Saboda haka wannan suna shi ne suna na tarihi amsasshe. Wani abu kuma da tarihi ya kawo ba siyasa ba, shi ne rashin ta da wani gari wajen kafa hedkwata. Fahimtar wannan lamari na da amfani sosai, kuma batu ne da ya cancanci maimaitawa matuqar gaske. Don kuwa ai tarihi yinsa ake yi, ba qirqiro shi ake yi ba.

Masana tarihi waxanda suka yi qulaficin bincike akan yadda aka kafa garin Kaduna sun ba da tabbacin cewa, an kafa wannan sabuwar hedkwatar Arewa a dajin doka wajen da babu gari ko qauye a cikinsa wato a budurwar qasa. A wani littafinsu, S. Bello da E. Oyedele sun jaddada wannan batun a cikin bayaninsu akan tarihin Kaduna inda suka ce: "an kafa garin a shekarar 1913 a qasar da babu kowa a Budurwar Qasa wato *Virgin land*, a wajen da yake da isasshan ruwa. "[3] Waxannan masana sun yi bayani akan asalin wannan waje, kamar haka: "Kaduna gari ne da ke cikin lardin Zazzau. Tun kafin Turawa akwai qauyukan qabilu da ke sassa daban-daban a Kudu da wannan gari. "

Akwai itatuwan doka masu yawa a wannan waje don haka ake kiransa dajin doka. Akasarin mazauna wannan wuri qabilun Gbagyi da Fulani ne, waxanda ke

---

1 *Cities of the Savannah (A history of some towns and cities of Nigerian Savannah)*, shafi na 63

2 E.O Oyewole, *Colonial Urbanisation in Northern Nigeria: Kaduna* 1913 - 1960, PhD Thesis (1987), shafi na 162

3 *Cities of the Savannah*, shafi na 63

zaune a gavar kogin Kaduna. Alal misali, akwai qabilar Gbagyi da ke zaune a Kudanda garin da aka fi sani da Kakuri a yanzu. A Arewacin wannan gari kuma, a kwai mazaunin Fulani da ake kira Kukogi, wanda ake kira Gworo a yanzu, wannan garin Fulani yanada nisan kilomita goma sha-biyar Arewa da Kaduna. Sauran wuraren da ke shiyyar wannan waje sun haxa da qananan garuruwa kamar; Jima, da Kaxi, da Kokau da Kadupe da Gwasonu.

Abin nufin a nan shi ne, samun mazaunin qabilar Gbagyi da wasu qabilu a wannan waje, wata alama ce da ke nuna cewa qabilar Gbagyi da wasu qabilu, su ne 'yan asalin wannan yanki wanda ya haxa da gefen garin Kaduna. Wata taqaddama a nan ita ce, Ko da yake waxannan mazaunin qabilun ba su da jama'a masu yawa, amma kamar Maqera na xaya daga cikin waje na farko dab da Kaduna ta kafu.

Wannan taqaitaccen bayani, ya nuna abubuwa uku da tarihi ya kawo: (1) babu gari ko qauyen wata qabila da aka tayar wajen kafa garin Kaduna, domin an kafa garin ne a *Virgin Land*. (2) Qabilun Fulani da Gbagyi su ne suka fi yawa a cikin qananan garuruwan da suka kewaye wanan *Virgin Land* inda aka kafa wannan garin. (3) Wannan bayani ya gasgata abin da Turawa ke faxi da cewa sun kafa garin ne a *Virgin Land* ba da nufin tauye haqqin wata qabila ba. Ita ma Miss *E.P. Miller*, Baturiyar Mishan ta ce zakoki ne a wannan daji saboda tabi ta wannan waje a shekarar 1907 wato shekaru biyar kafin a fara gina garin Kaduna a dajin Doka.

Iqirarin da ake yi daga baya, na cewa an tarwatsa garuruwan qabilar Gbagyi, a dajin doka da ke wannan waje ba tarihi bane, wata siyasar maida abin wani naka ne, ake son kawowa. Saboda a cimma wani buri na siyasa da qabilanci. Haka kuma Turawa ba sunyi amfani da kalmar *Virgin land* don su mallaki waje bane. Ai wanda ya mallaki qasa baki xayanta, mallaka waje ba zai masa wuya ba. Saboda an ce, kai da kaya ai mallakar wuya ne. Abin da ya sa su faxin haka, domin gudun zalunci ne. Saboda haka sai suka faxi gaskiya, wanda sunanta gaskiya.

Kamar yadda aka yi bayani kuma abin maimaitawa sosai babu wani gari da aka ce an tayar wajen kafa Kaduna. Tarihi ya nuna babu wani gari na Fulani ko na Gbagyi ko na wata qabila da aka tayar don a kafa garin Kaduna. Turawan mulki, mutane ne masu ilimi da hangen nesa. Wannan wuri ya cika manyan sharuxxa guda uku, da ya sa suka kafa sabuwar hedkwata. Na farko, shi ne rashin samun wani gari a dajin Doka. Ana gudun tayar da wani gari don kafa sabuwar hedkwata bai dace ba domin yin haka zai kawo qorafe-qorafe da fitinu na siyasa. Saboda daga baya qabilar wannan gari za ta iya neman aba ta garinta, ko a jima ko a daxe. Turawan mulki sai suka yi sa'a da katari da samun dajin doka. Saboda haka sai aka kafa gari, a dajin doka wajen da ba shi da wani gari wato, *Virgin Land* kamar yadda Turawan suka kira wannan wajen da suka samu.

Wannan ya dace sosai da tarihi da bincike tabbatacce, don kuwa idan akwai wani gari a wannan waje da tilas ya zauna a qarqashin mulkin Kinkinau ko Maqera, da kuma tilas ya riqa kai harajinsa Zariya, tushen mulkin Zazzau. Kamar yadda sauran garuruwa ke yi a wancan zamani. Hasalima, da ace Turawa sun tarar da wani gari da sun rubuta a kundin tarihi da ake rubutawa na shekara da shekara, wato *Annual Report*, wanda su kan rubuto kamar rahoton duk abubuwan da suka auku a kowace shekara ga hukumar mulki. Haka kuma da an faxi sunan wannan gari da aka samu da kuma sunan sabon waje da aka koma da su, tare da kuxin diyyar da'a ka biya su.

Turawan mulki ba sa nuna zalunci varo-varo, irin wanda ake zarginsu da shi wajen kafa wannan gari, kusan shekaru xari da suka shuxe. Ana zarginsu da zaluncin tarwatsa garuruwan Gbagyi da ke wannan waje, a cikin fafitikarsu ta kafa garin Kaduna kwatsam! Sai aka ce Turawa sun sami gari cike da jama'a, sai suka tarwatsa garin ba da sunan yaqi ba, amma da sunan neman wurin zama. Don matuqar nuna zalunci ma ko diyya masun qi su biya! Wannan batu ba tarihi ba ne, siyasar qabilanci ce tsagwaranta.

An yi amfani da wani bincike mai sunan tarihi, an kuma yi rubuce-rubuce a mujallu da jaridu masu yawa inda ake ta kuka da qorafin wannan zalunci, da aka ce Turawan mulki sun tafka, wajen kafa garin Kaduna. A wani soki-burutsu na wani kundi cewa aka yi: "Akwai mazaunar qabilar Gbagyi a Bugai da Rido da Afago da Barnawa da Kurmin Kaduna, wanda yake da ganuwa da jama'ar gari masu kimanin yawan xari uku (300). "[1] Wani abin ban mamaki da wannan bayani, shi ne wai an samo shi ne daga cikin rahoton Soji na shekarar 1912 wato *Military Report of 1912*. Waxanda suka ba da wannan rahoto ba su bambance garin Gbagyi da na sauran qabilu ba. Don kuwa ta yaya za su haxa garin Barnawa, wanda Barebare da Fulani suka kafa su mai da shi garin Gbagyi? Wannan shi ne hankaka maida xan wani naka.

Haka kuma wane gari ne "Kurmin Kaduna " da yake wannan wuri a shekarar 1912 wanda Zazzau ba ta sanshi ba? Haka dai aka ce Turawa sun tarwatsa wannan qabila a wannan tsohon gari, da ke zaune a garinsu na asali domin su samu wajen kafa Kaduna. Idan da haka ne, kana iya cewa garin Kaduna ya samo sunansa ne daga "Kurmin Kaduna. " Don kuwa wannan garin Gbagyi mai suna Kurmin Kaduna amma ba "Kurmin Kadundna ba. " A qashin gaskiya wannan gari ba shi a tarihi, wato "fatalwar " gari ne don ba wanda ke ganinsa ballanta ya san shugabaninsa da masarautar da ke da iko da shi. Wannan misali ne babba na qoqarin qirqiro tarihi don biyan wata buqata ta siyasa. Tarihi ya san da Kurmin Gbagyi da Kurmin Mashi amma bai san da Kurmin Kaduna a kusa da dajin doka ba. Ta haka ne ake sauya sunayen wurare don a birkita tarihi.

---

[1] E. O. Oyewole, *Colonial Urbanisation*, shafi na 164

Haka kuma an ce bincike ya nuna da cewa qabilar Gbagyi ta shigo wannan yanki ne a qarni na goma sha-huxu wato "14th Century A.D, " a lokacin da suka watsu, zuwa waxannan garuruwa da ke sashen kogin Kaduna, a wannan kundi cewa aka yi:

> *Garuruwan sun haxa da Barnawa da Kurmin Mashi, Rigasa da Kupei. Amma shi garin Kupei yana wajejen inda Gidan Yari wato "Kaduna Prison " yake a kan titin "Independence Way. " An kuma samu wata tsohuwar rijiya a wannan wuri, tun kafin zuwan Turawa, a layin Kanta, a kuma farfiyar Bataliyar Soja ta farko a yanzu wato "The First Infantry Battalion Mess. " Akwai kuma mazaunin wannan qabila wato "Settlement, " da ake kira Palihi a wajen da babbar kasuwa take a yanzu, akwai wasunsu kuma a wajen Kabala. Haka kuma akwai mazaunin wannan qabila, a wuraren da ba su wuce nisan kilomita talatin (30) da Kaduna ba, waxanda suka haxa da: Dan Hono da Tokache, da Bugai da Kujama da Gwagunu da Kanrafi.*[1]

Har-ila-yau an ce akwai ire-iren waxannan wurare a Arewa da kogin Kaduna. A kuma wajejan Kawo, akwai masaukin fatake a sassa da dama.[2] A waxannan wurare ne fatake ke haxuwa, idan sun fito daga qasashen Hausa za su Gwanja ko Kurmi wato kudancin wannan qasa, don sufuri da kasuwanci.

Duk waxannan mazaunai na Gbagyi ba su da nasaba da Kaduna. Ba wanda ke tantamar rashin mazaunin qabilun Hausawa da Fulani da Gbagyi, a waxannan sassa da ke kewaye da dajin doka. Abin da ake buqata shi ne samun gari a cikin garuruwan Gbagyi da aka tayar, amma ba mazauni da ke maqwabtaka da wannan waje ba, mai kuma nisan kilomita talatin daga dajin Doka.

Kaqiqka an san akwai garuruwan da ke kewaye da Kaduna waxanda suke da ganuwa tun shekaru masu dama, kafin zuwan Turawa wannan yanki. Tsofaffin garuruwan su ne Barnawa, da Maqera da Kakuri Kurmin Gbagyi, da Kinkinau (Kangiwa) da Kurmin Mashi. Waxannan su ne garuruwa masu ganuwa da suka kewaye Dokar Dajin da aka kafa garin Kaduna, da shigowar Turawa Arewa. Garin Barnawa shi ne mafi daxaxxan tarihi a wannan yanki.

An kuma san tsofaffin garuruwan Gbagyi, an fi samun su a lardin Neja. A nan ne aka ce sun zauna a lokacin da suka fito daga qasar Barno, kafin Nagwamatse ya tarwatsasu zuwa lardin Zazzau. A yankin Neja suna da yawa, inda suka kafa garuruwansu a Kuta, da Galadiman Kogo, da Fuka, da Guni, da Gini, da Sarkin

---

1 Enoch O. Oyedele, *Colonial Urbanisation: Kaduna 1913* – 1960, shafi na 166

2 Abdulqadir Y. Sambo, *Qasidar Tarihin Garin Kaduna*, shafi na 4

Pawa, da Dangunu, da Allawa, da Bosso, da Erena, da Maikunkele, da Minna, da Manta, da Gussoro, da Paiko! [1]

Tarihi ya nuna cewa, Gbagyi 'yan asalin qasar Barno ne; daga nan ne suka fito zuwa lardin Neja.[2] A wannan waje, sun zauna da qabilun Koro, da Bassa, da Kadara, da Kamuku da Hausawa. Da aka tarwatsa su, a lokacin yaqe-yaqe sai suka kwararo zuwa lardin Zazzau inda suka samu zama na lumana tare da Hausawa da Fulani, sai abin da ba a rasa ba. Saboda a wannan lokaci na yaqe-yaqe ne don haka suke zama a "Kurmi " wato *Forest* don samun qarin tsaro. Daga kurmi ne su kan fito su yi xaixaikun gidaje ko bukkoki a cikin daji musamman a kefen dajin doka.

Don kuwa idan wani mutum ya baro garinsa alal misali, da ke Kurmin Mashi, ya zo jeji da iyalansa ya kafa gida ko bukka ya zauna, yana da ikon zaunawa a ko'ina ya kuma kafa mazauninsa amma ba a bisa doka ba. Wannan mazauni ne amma ba gari ba. Idan hukuma za ta yi amfani da dajinta, sai a tashe shi ya koma garinsa ko qauyensa. Saboda haka tashin mazauni ba dai-dai yake da tashin gari ko qauye ba. Haka kuma, idan Bafilatani ya baro garin Kawo, ya kafa rugarsa a daji yana da ikon yin haka. Shi ma tashinsa ba dai-dai yake da tashin qauye ba.

Dukkan wuraren da ake kururuwar an kafa su, ba su kusa da jejin da aka kafa Kaduna. A duk wuraren da ke yankin Kaduna, a kuma duk inda ka samu mazaunin Gbagyi wato *Gbagyi Settlement* za ka samu yana maqwabtaka da mazaunin Fulani wato *Fulani Settlement* wanda aka fi sani da Rigar Fulani. A bisa dokar qasa kuwa mazauni wato settlement ba shi da darajar qauye domin ba shi da ikon mallakar qasa kamar gari ko qauye. Har ila-yau kada a manta da dangartaka ta qut-da-qut da ke tsakanin Fulani da Gbagyi.

Dangantakar maqwabta tsakanin Gbagyi da Fulani a wannan wuri, wata irin maqwabtaka ce ta manoma da makiyaya, wacce babu fitina da hargitsi sai nuna qauna tare da taimakekeniya. Amma saboda mahibbar Gbagyi idan aka gansu a wuri tare da Fulani, ganin na su ake ruwaitowa, wataqila ba a xauka rubuta cewa an ga rugagen Fulani a wurare daban-daban, ba abin da ya kamata a rubuta bane. Babu inda zaka ga mazaunin Gbagyi ba ka ga na Fulani kusa da shi ba. Yanzu ne ake raba su, amma maqwabta ne na qut da qut a wancan lokaci. Don kuwa har kariya Fulani ke ba su idan Hausawan garin Afaka sun nemi akai haraji. Saboda tsoron kada "Tuwa " ya ci su, ya sa Gbagyi ke ravar Fulani don zamantakewa mai amfani da sahalewa.

---

[1] NSAM: APN/695 Niger Province (*Geography, History and Notes on the Division*). 1950, shafi na 1.

[2] HD Gunn and F.P Connant, *People of the Middle Niger Region of Northern Nigeria Forde* W.A. Institute, London, (1960) shafi na . 109-110.

Amma ba mazauni ne kawai waxannan qabilu suke da su ba, suna da garuruwansu da ke kewaye da dajin doka, kamar yadda aka yi bayani a baya, karakainar Fulani da Gbagyi a gavar kogin Kaduna da dajin doka abu ne da zai baiwa mai binciken tarihi sha'awa. Saboda gallazawar Hausawan Afaka masu mulkin qasa tun kafin zuwan Turawa, ta haddasa ta kuma assasa abokantaka tsakanin Fulani da Gbagyi, ba domin komai ba sai don su taru su kare kansu, a lokacin mulkin mai qarfi sai Allah Ya isa!

Akwai wani abin fahimta a nan, shi ne na garin Barnawa a matsayin babban gari da ya yi suna wajen yaxa ilimin Qur'ani Mai girma. Saboda haka ta dajin doka ake kaiwa da komowa musamman tsakanin Birnin Zazzau da garin Barnawa, wanda daga baya ya zama cibiyar Sarakunan Zazzau daga mulkin Fulani. Don haka da wuya a samu wani garin Gbagyi a wajen gwadaben da 'yan jihadin Daular Usumaniyya ke karakaina a tsakanin waxannan garuruwa. Saboda haka zaman wannan qabila a tsallaken kogin Kaduna ta Arewa sai da kariyar maqwabtaka ta Fulani.

A inda qirqirar tarihi zai ci tura, to, sai a kawo haxakar tarihin wurare a cava su waje guda domin cimma wani buri na siyasa. Alal misali, akwai qoqarin haxa tarihin wannan yanki na Arewacin kogin Kaduna, da qauyuka, da garuruwan Cikun da Kujama waxanda suke fitattun garuruwa ne na Gbagyi. Saboda idan aka gwama tarihin, aka kuma murjeshi shi ya zama xaya, to, yin haka zai baiwa qabilar Gbagyi wani qarfi na siyasa. Wannan zai ba su qorafi da murya babba wajen gwagwarmayar cewa, a ba su garin da Turawa suka tarwatsa su don kafa Kaduna. Amma tarihi shi yin sa ake yi, ba qirqiro shi ake ba. Don haka ba yadda wannan haxakar za ta haifar da xa mai idanu, domin hakan ba zai yiwu ba. Ba kuma yadda garuruwan qabilar Gbagyi da ke kilomita 30 daga Kaduna za su yi tasiri akan tarihin wannan gari.

Domin haka ne ake qoqarin gwama tarihin wannan gari da na: Danhono da Tokache, da Bugai da Gwagunu da Kanrafi, yin haka ko da ta misali bai dace ba saboda babu wani gari da har yanzu da za a ce an tayar da shi don kafa Kaduna. Waxannan garuruwa kuma nesa suke da garin Kaduna. Tarihi ya nuna fitattun garuruwan Gbagyi da ke nesa da Kaduna sun haxa da Ruhoji da Kudanda da Kaban da Rafin Kura da Kawu da Gwaraji da Katura da Togwaye da Kamasu da Waje da Gaina da Rido da Damashi da Mafura da Kapaya da Gadani da Maru da Gora da Kakau Daji da sauransu. Ko, da ma an ce Zazzau masomar Gbagyi.

A wannan yanki da ke kusa da Kaduna babu fitaccen garin Gbagyi kamar Kakuri Kurmin Gbagyi. Akwai fitattun garuwan Gbagyi waxanda yawancinsu a Kudu da kogin Kaduna suke. Alal misali, Yamma da Kakuri Kurmin Gbagyi akwai waxannan garuruwa: Kudan da Matari da Ligari da Kagurna da Gudarife da Kukau da Gwazunu da Gadani da Katari da Katarma da Cikun da Kasaya da

Gwani-Gwara. A Kudancin Kakuri kuma, a qwai garurunsu kamarsu: Kujama da Bugai da Tokake da Kashavo da Kugu da Kashurmu da Gwaraji.

Wani abin lura shi ne yadda qabilar Gbagyi da Fulani su ka watsu a gavar kogin Kaduna kafin vulluwar Turawa, amma kuma ba su kafa gari a dokar daji ba. Qabilar Gbagyi sun fi yawa a Kudu da wannan kogi. Fulani kuma sun fi yawa a Arewacin wannan kogi. Saboda bambancin sana'a, manoma na neman qasa mai albarka makiyaya kuma na neman wajen da ke da isasshen ruwa da ciyawa.

Haka kuma abin lura a nan shi ne Gbagyi sun fi yin mazauni da qauyuka da garuruwa Kudu da kogin Kaduna fiye da Arewacin wannan yanki. Akwai dalilan da suka haddasa haka, domin ya kamata ne a same su a Arewaci kamar yadda suke a kudancin kogi. Wani dalili da ake bayarwa shi ne rashin samun isasshen qasar noma mai kyau. Wannan hujjar ba ta da qarfi sosai. Amma hujja mafi qarfi ita ce zaman mage da vera da ke akwai a tsakanin mutanen Afaka da Gbagyi har ma da Fulani. Don kuwa matsananciyar addabar mutanen Afaka, mai yiwuwa nema da fargabar ganin karakainar 'yan jihadi da ke kaiwa da komowa a tsakanin Birnin Zazzau da garin Barnawa.

A qoqarin tabbatar da wani garin Gbagyi a dokar dajin doka, wai wani bincike ya nuna cewa, M. Cameron Blair, Jami'in Tsabta wanda ya zauna a yankin Kaduna, kafin shekarar 1913 ya ruwaito cewar akwai Mazaunai wato *Settlements* a wannan yanki.[1] An yi mazauni Kupei a inda a ka gina Gidan Yari wato 'Kaduna Prison'. Ai babu mai shakkun samun jama'a a wannan yanki, a geffen dajin doka Amma Cameron Blair bai fayyace qabilun waxannan mazaunan ba, ko Fulani ne ko Gbagyi ne ba. Saboda haka ba za a ce kai tsaye mazaunin Gbagyi ne ba sai da hujja mai gamsarwa. Saboda gwarawa da Fulani maqwabta ne a wannan waje. Sannan kuma ba a faxi inda wannan Jami'i yake zaune ba, a gari ne ko daji. Domin a wanan lokaci ne ake gina garin Kaduna jama'a ba su tare ba.

Haka kuma wannan mai bincike ya ce, mazaunin Gbagyi a yankin Kaduna kamar yadda wasu, ke faxi sun haxa da Barnawa da Kurmin Mashi da Rigasa da Kupei. Ya qara da ba da misali da wata rijiya da ke kan titin "Kanta Road " a harabar soja ta *First Infantry Battalion Mess*. Sannan ga mazaunin Gbagyi da ake kira Palihi da aka ce yana wajen da aka kafa babbar kasuwar Kaduna a yanzu.[2]

Wajen da ake raxe-raxin an samu tsohuwar rijiya, a kan titin Kanta kuwa mai yiwuwa zango ne da ke kan gwadaben 'yan jihadin Daular Usumaniyya. Wannan waje gwadabe ne na fatake da baraden yaqin jihadi. A nan za su sauke kansakalinsu, su kwance sirdinansu a wannan zango. A wannan rijiya suke samun ruwan sha, da na Sallah, in sun fito daga Zariya zuwa Barnawa da sauran wurare da ke maqwabtaka da wannan daji. Haka kuma mazaunin na Gbagyi da aka ce

---

[1] Enoch, O.O., *Colonial Urbanisation*, shafi na 163.

[2] *Ibid.*, shafi na 166.

yana Palihi ba zai rasa maqwabcin mazaunin Fulani ba. Hasali ma dai, akwai ire-iren waxannan wurare da suke Zangon Fatake ne ga 'yan kasuwa masu zuwa fatauci zuwa garuruwan da ke kudancin Arewa.

Mista K.J. Bryant Babban D'io na lardin Zazzau ya ba da tabbacin cewa babu wani gari da aka tayar a dajin Doka wajen kafa wannan sabuwar hedkwata, domin yin haka zai kawo fitina daga baya. To ga shi ba a ta da garin kowa ba amma yanzu qoqari ake yi, a qirqirowa Kaduna sabon tarihi, ba domin komai ba sai domin haddasa rikici na siyasa da qabilanci. Abin da ba a son a faxi, shi ne tarihi ya nuna cewa ba a tashi wani gari ba, wajen kafa Kaduna. Wannan batu ne da wasu ba sa son su ji. Anan, sai a maimaita da cewa, tarihi yinsa ake yi, amma ba qirqiro shi ake yi ba. Ai gaskiya sunanta gaskiya.

Dalili na biyu na dacewar Kaduna shi ne ba a matsi masarautar wani Sarki ba, wanda zai iya kawo takunsaqa tsakanin Turawan mulki da masauratar wannan Sarki. Saboda Kaduna ba ta matsi Zariya tushen mulkin Zazzau ba, sai ta dace da zama sabuwar hedkwata.

Xan wurin da ake kira Kaduna wani taqi ne mara girma. A taqaice yana tsakanin tashar Jirgin Kakuri, "Kaduna South Junction " wanda aka fi sani da Kaduna Jamsin, da "Kaduna North Junction " wato tashar Jirgin Arewacin kogi. A wannan tsakatsakin garuruwan Kawo da Kinkinau da Kurmin Mashi daga Arewacin kogi. Sannan kuma da Maqera da Kakuri Kurmin Gbagyi da Barnawa da ke kudancin kogi, aka kafa garin Kaduna. Domin haka waxannan garuruwan sun girmewa Kaduna nesa ba kusa ba. Su ne kuma garuruwa da ke kewaye da shi.

Wannan sabon gari kuma bai kusanci manyan garuruwan wannan zamani ba kamar garin Rigacikun da Afaka. Saboda haka ba a samu wani taqun-saqa wajen Mulkin Mallaka ba. Amma duk da haka waxannan tsofaffin garuruwa sun ba da gudunmawa sosai wajen bunqasarsa da mulkinsa don samun ci gaba.

Daga qarshe, sai a qara nanata batun kyawon yanayi. Komai kyawon wajen idan zai kawo wata barazanar rai ko tsaron jama'a ba zai samu karvuwa ba. Amma yanayin wannan waje mai kyaune ga zahiri, amma duk da haka sai da Gwamna Lugga ya fara girke Sojojin WAFF a garin Barnawa a shekarar 1913 don qarin tsaro da gwajin yanayi. Saboda dangartakar waxannan garuruwa da dajin doka babu yadda za ka hana Fulani makiyaya da Gbagyi manomafitowa a xaixaiku don kafa mazaunin kiwo ko bukkar gonar noma a wannan daji.

Ko da yake Fulani sun fi mazauni a rugage da yawa kamar yadda aka san su da yawace-yawace neman wajen kiwon shanu amma abin takaici ba a faxansu a wajen bada tarihin wannan waje. Wata qila, an xaukesu baqi ne. Amma qabilar da tafi shekaru xari uku a wurin kafin vullowar Turawa, ta kuma kafa garuruwa manya ta fi qarfin matsayin baqunci, a yankin kogin Kaduna da dajin Doka da ke Arewa da shi. Saboda kyakkyawar dacewar wannan sabon wuri da kuma hangen

cewa, kafa gari a cikinsa wato *Virgin Land* ba zai kawo fitinu daga baya ba, sai aka tashi haiqan wajen qafa garin Kaduna.

Turawan mulki sun sami misalin shekara goma una neman wajen da za su kafa hedkwata wadda ta dace. Rashin samun wani qauye ko gari a dajin Doka, yana xaya daga cikin dalilan zaven wannan waje. Saboda tsoron kada abar baya da qura. Don kuwa idan aka tayar da wata qabila wajen kafa hedkwata, zai haifar da qorafi daga baya saboda wannan qabila ka iya tada qayar baya tace a bata wajenta ko kuma a biya ta diyya. Haka zalika, mazauna wannan hedkwata za su yi ta fama da qwarzabar wannan qabila saboda qwanji da mayata. Duk qoqarin da ake yi shi ne na faxin gaskiya al'amari ba nema ake a danne haqqin wata qabila ba . Babu wani qauye ko gari da aka tayar a dajin doka don kuwa gaskiya ai sunanta gaskiya. An samu sa'ar dacewar kafa garin Kaduna a virgin land, wato budurwar qasa a dajin Doka.

Qanwar Baturen Mishan Likita Miller mai suna Miss E. P. Miller ta jaddada gaskiyar cewa babu gidaje a dajin da aka kafa garin Kaduna. Wannan sananniyar Baturiyar ta Mishan, ta bayyana yadda al'mura su ke a da, a lokacin da suke tafiya a qasa a wanna waje, a shekarar 1907 wato shekaru biyar ke nan kafin a kafa garin Kaduna, inda ta ce:

> *Muka qetare Kogin Koriga, kusa da inda shi ne hedkwatar gwamnati a yanzu a Kaduna. A lokacin nan babu gidaje, sai dai akwai 'yan Zakoki Kaxan – ba irin Zakokin nan da su ke cikin manyan gidaje masu kyau a yanzu a wurin ba ."*[1]

A farkon shekarar 1954, Miss E. P. Miller, ta yi magana a rediyo inda ta bayyana wahalhalun da suka sha a farkon shigowarsu wannan qasa a shekarar 1907. A wannan lokaci ne ta bada gaskiya! shaidar cewa wajen da aka kafa Kaduna daji ne babu gidaje sai zakoki. Saboda haka babu yadda za a a kafa gari a gandun dajin zakoki, ai gaskiya sunanta gaskiya. Shi ma wani tsohon shugaban kwalejin Kaduna Mr. Mort ya bayyana yadda al'ummaran wannan jiha yake a da. Irin wannan taqaitaccen tarihi da tsofaffin Turawa ke bayarwa na da amfani matuqar gaske. Domin a idonsu ne aka yi abubuwa muhimmai, a farkon shigowar Turawa wannan qasa.

Yadda Al'amura Su Ke Da

Mr. E.L Mort, babban Baturen Kwaleji ta Kaduna a da, ya koma Ingila. Ya zo qasar nan takanas, domin a yi bikin Itisi ta Toro da shi, don kuwa shi ne ya kafa ta. Kafin Mr. Mort ya shiga jirgin sama zuwa *London*, sai da ya yi magana a

[1] GTK, 10/3/1954, shafi na 6

wayar iska. Ya bayyana godiyarsa ga jama'a, kuma ya tuna da yadda al'amura su ke sa'ad da ya fara zuwa qasar nan, bayan shekara wajen arba'in da suka wuce. Mr. Mort ya ce:

"Sa'ad da na sauka a jirgin sama a Kano, na shiga mota na ratsa hanyoyin Kano, ga su cike da jama'a da alamar arziqi, wannan har ya sa na tuna da yadda al'amura su ke da, lokacin da na fara zuwa qasar nan, yau shekaru kusan arba'in. Sa'an nan na sauka a Kano a jirgin qasa, amma sa'an nan babu tasha, sai kawai jirgi ya tsaya, mutum ya sauka ya ratsa gonakin gero da dawa ya nufi inda za shi. Da na sauka na hau doki zuwa masaukina – 'yan xakuna biyu na ciyawa. Ina tsammanin dai-dai ne idan na ce lokacin nan babu mota ko xaya a Kano, babu kuma arziqi kamar yanzu, domin kuwa Jihar Arewa ta fita cikin shekarar da aka yi muguwar yunwan nan ke nan.

"Da zan zo qasar nan na shigo cikin jirgin ruwan da a ke kira "Elmina, " tare da shahararren mutumin nan Gwamna Lugga. Sa'ad da muka iso Ikko sai jirgin mu ya tsaya daga can nesa, sai 'yan qananan jirage suka kwaso mutane da kayan mu zuwa Iddo, domin a lokacin ko alamar Apapa bubu, sai fa a takarda. A Iddo ne fa muka fara shan wahala wajen kintsa kayan mu. Ni kaina ina da kaya wajen qunshi 50. Domin sa'an nan tilas mutum ya zo da kusan komai yake buqata daga Ingila. Ana daxewa qwarai a hanya tsakanin Ikko zuwa Kano lokacin nan, fiye da yanzu. Sa'an nan ba a qare gadar Jaba ba. In an iso wurin sai a yi fiton fasinja da kayansu cikin qananan jiragen ruwa zuwa gava inda za su sake shiga jirgin qasa. Irin waxannan jiragen ne aka yi amfani da su a Makurxi.

"Bayan na yi 'yan kwanaki a Kano, sai kuma aka aika da ni zuwa Sakkwato, Na kuwa kwashi 'yan dako masu yawa, ka gan mu ba mu isa Sakkwato ba sai bayan wajen kwana ashirin da xaya. Ni kaina ina bisa doki, wani irin hutsun doki – ga ni kuwa ban san komai ba ta doki. Na saye shi da kuxi da yawa fiye da yadda ya kamata a Kano. Wannan tafiya da gajiyarwa take. Amma duk da haka na koyi wani abu cikin harshen Hausa, domin in ba haka ba, sai in yi ta tafiya haka nan cikin jama'a kamar kurma, su suna maganarsu ba na jin abin da su ke faxi. A sa'an nan kuxin dako kwabo tara ne ko wace rana. Mil wajen 300 muka yi tare da 'yan dakon nan. Sa'an nan shekara takwas ne bayan yaqin Satiru a Sakkwato.

"A lokacin nan ne Yaqin Duniya na na Farko ya tashi. Bayan na xan jima ina aiki a Birnin Kabi, cikin watan Fabrairun shekarar 1915, na tashi daga nan zuwa Lakwaja, domin in shiga soja. Na kama hanyar zuwa Zungeru, wadda sa'an nan ita ce babban garin Jihar Arewa. A nan na shiga jirgin qasa zuwa Baro, sai kuma na shiga jirgin ruwa. Duka na yi fiye da mako huxu ina tafiya. Wato dai wata shida na farko da na yi a qasar nan kusan in cewajen tafiye-tafiye na vata su. Gara ni ma da xan dama-dama bisa ga waxansu Turawan mulki da suka fara

zuwa, irin waxanda a ke aikawa da su wajen su Barno, kafin a yi hanyar jirgi. Domin mai yiwuwa ne su vata wajen rabin lokacinsu na aiki wajen tafiye-tafiye zuwa wuraren da aka ce za su zauna.

"Hanyar da na biyo daga Sakkwato tana ba ni sha'awa. Domin hanyar shanu ce daga Sakkwato ta bi kwarin Kogin Neja zuwa wajen Ikko. Ko yaushe akwai mutane jingim a kanta, kamar dai yadda ko wace hanyar mota ta zamani ta ke a yanzu. Har ma na manta da zan tafi yaqi ne, sai bayan da na yi wata takwas a Lakwaja, sa'an nan na fita. Ina can ne aka wuce da kayan faxa cikin kogi zuwa Garua, inda aka cewai qarar bindiga ce kawai ta sanya wata qungiyar Jamusawa suka xaga tuta, suka bi.

"Aka ba ni qunshin kaya 500 na makamai, irin na Faransa, aka ce in kai wa sojan Janar Cunliffe, lokacin nan sun tashi daga Garua sun tasar ma wajen Kudu, domin su haxu da sojan da su ke faxa a kudancin Kamaru. Na shiga cikin jirgin ruwa har zuwa Bakundi, a cikin Kogin Taraba. Sai kuma muka damqi qasa, mu hau wannan tudu, mu gangara wannan kwari, muka kewaya ta Gashaka har zuwa Banyo, wajen Kudu kusa da Kogin Sanaga. Babu shakka tafiya da leburori 500 a cikin qasa, wadda ta ke ana tashin hankali cikinta, aiki ne babba. Amma duk da haka sun yi yadda a ke buqata. Sa'an nan babu kadarki a koguna. Jamusawa duk sun kwashe abincin da ke qasar. Mutanen qasar sun tsorata duk sun vuya. Don haka tilas ne mu xauki duk irin abincin da za mu ci. Mu duk muka rage cin abinci, har da ni kaina. Kullum daga 'yar shinkafa, sai 'yan karo-karo. A Banyo Jamusawa suka yi babbar tasharsu. Ga tare-mahawa, ga soja ko yaushe suna ta sintiri, da sauran alatu dai. Amma da sojan Janar Cunliffe suka tunkari wurin, ai nan da nan sojan Jamus suka watse, suka haye Tudun Banyo, waxansu suka shiga cikin koguna. Daga bayan qungiyar Arewa ta yi irin nata aiki, sai aka bar ni a Banyo don in qidaya ganimar da aka samu. Na yi wata xaya a nan. Amma lallai na yi mamakin yadda suka shirya wannan wuri don amfanin kansu kawai. Har ma mun ga wata kati, irin mai kamar keken dokin nan, ta macen da ta ke Gwamna, wadda aka kawo ta tun daga bakin ruwa, misalin mil 300. Kusan ko ina mutum ya shiga cikin qasar zai ji waxansu suna magana da turanci irin na barki.

"Zama cikin Nijeriya ya fi daxi a lokacin nan, a kowane hali kuwa a nan Jihar Arewa. Babu wata hanyar tafiya mai sauri im ba bisa doki ba, don tilas ne. Amma kuma akwai waxansu lokutan da za a buqaci wani abu mai sauri fiye da doki, tun ba ga likitoci ba. Na tuna wani likita a Bauci ya hau doki ya yi mil xari ba tare da ya tsaya ko ina ba, domin ya je ya ga wani Di'o wanda ba ya da lafiya. In doki xaya ya kasa, sai kuma ya ari wani ya ci gaba har zuwa wani zango. Bai tsaya ko'ina ba wai don shi ya huta. A halin haka wani lokaci sai ka ga likitan ya sauka da rashin lafiya fiye ma da mara lafiya xin da ya je dubawa.

Sa'an nan ta hanyar kada-ta-kwana a ke xaukar wasiqa mail. In an bai wa wannan manzo, sai ya yi gudu ya kai wa wancan, shi kuma ya ci gaba. Har a kai takardu inda a ke buqata.

"Sa'an nan babu rubuce-rubuce da yawa bisa takarda, babu zama ofis da yawa. Turawa sun fi aiki fiye da yanzu. Da aka fara shigowa da mota Fodu, wadda ta ke iya shiga ko ina, sa'an nan ne abubuwa suka fara canjawa, komai ya soma sauri. Har ga shi yanzu zamanin nan na da mai daxi ya wuce. Babu yadda za a yi mutum ya kasa tunawa da irin waxannan lokuta."[1]

[1] GTK, 3/2/1954, shafi na 5

KASHI NA HUXU

Kafa Garin Kaduna

Zirga-zirgar jirgin qasa a tsakanin Baro zuwa Kano ta yi nisa a cikin shekarar 1911 zuwa 1912. Wannan ya bai wa Turawa damar ganin ni'imar da Allah Ya yi wa jejin doka da ke Gabas da hanyar jirgi, da Arewa da gadar jirgin kogin-Kaduna. Wannan abu ya sa Turawa gode wa Allah domin abin nema shekara da shekaru ya samu, wato wajen da zai dace da zamansu. Wannan dajin doka da suka gani zai dace da kafa hedkwata, zai yi kuma kyau da muhallinsu.

A dalilin haka sai aka yiwa wannan waje qulaficin bincike domin a tabbatar da da dacewarsa da kafa gari. gwamnatin Mulki sai ta turo masana fanonin kafa gari daban-daban, kowannen su kuma aka buqaci ya aiko da rahoton bincikensa. A wannan shiyya da Gwamna Lugga ya zava da ya kafa hedkwatar Arewa ko kuma ta qasa baki xaya sai ya rubuto a rahoton sa, wato *Amalgamation Report* wanda ya aikawa Sakataren kula da qasashe da ke qarqashin Ingila, a watan Mayu na shekarar 1913 a inda ya yi taqaddama da cewa: "Zungeru ne gari da ke tsakiyar qasa wadda ake saurin kaiwa gare shi. Amma garin ya gama biyan buqata saboda yana da matsanancin zafi, da duwarwatsu, ga shi kuma da yawan sauro mai addabarwa. Domin haka na ba da umarni da a tashi daga wannan hedkwata, a koma da ita dai-dai wajen da hanyar jirgi ta qetare kadarkon jirgi a kogin Kaduna, wanda yake da nisan mil 572 daga Ikko. "[1]

gwamnan bai vata lokaci ba sai ya aiko da rundunar sojan WAFF da ya kafe a Zariya tun a shekarar 1913 da su taso zuwa garin Barnawa, don su zama zakarun gwajin-dafi, wajen dacewar wajen da za a kafa gari. Ya kuma umarci kwamandan wannan rundunar soja da ya lura da waxannan abubuwa:

"Ya rubuta tashi da faxuwar ruwan kogi da gudanarsa, da ya cike duk wuraren da ruwa zai taru da, xaukewar damina, da ya kawar da duk wuraren da qudan tsando da sauro za su hayayyafa da, ya kuma lura da lafiyar sojansa, da tsinkayar dacewar wannan waje da kafa hedkwata. "[2]

Saboda da waxannan abubuwa da Gwamna ya sa a lura da su a Barnawa, sai Jami'i mai aikin sirri, Leftana *Agibson Craig* da ke rundunar WAFF ya aiko da rahoto a watan Yuli na shekarar 1913. A rahotansa ya cewajen na da ruwan sama mai inci 11.8 da awon zafi wato *temperature* 75.11^0F. A watan Agusta da Oktoba

---

1 Kirk – Greene (ed), *Lugard and the Amalgamation*, shafi na 93

2 NAK. SNP 7 3854/1913: JB. Cockburn Ag. Commandant of the Northern Nigeria Regiment

ruwan sama na da inci 11.53 da 11.7 a waxannan watanni, yana kuma da madai-daicin zafi, mai awo 75.6^0F da 78.0^0. Wannan bincike ya nuna dajin doka da ke yankin kogin Kaduna ya fi Dungurun samun isasshen ruwan sama. Ko da yake wannan waje na da sauro masu yawa, amma sojojin wannan runduna suna zaune cikin qosasshiyar lafiya.[1]

A binciken Jami'i mai kula da Tsabta, *Dr. H. Andrew Foy*, shi ma ya ba da rahotonsa da ya yi binciken wannan waje a shekarar 1913, domin ya tabbatar da wajen zai dace da zaman Turawa. Wannan Likita ya yi bincike mai zurfi inda ya ba da rahotonsa a jaddawali a inda ya kwatanta yanayin Kaduna, da Zariya da Kano, da Dungurun na tsawon watanni bakwai.[2] Kulaficin binciken wannan likitan Tsabta ya qara tabbatar da dacewar Kaduna. Saboda haka aka tashi gina Kaduna sabuwar Hedkwata da gaggawa. Binciken farko da aka yi da ya nuna dacewar wannan waje shi ne na *Mr. Lamb*, Daraktan Aikin Gona da na *Mr. Eaglesome* Daraktan Ayyuka. Shi Lamb cewa ya yi Kaduna a wajajen rafukan Barnawa guda biyu, yana da yanayin qasa mafi kyau a duk faxin Nijeriya. Mr. Eaglesome shi kuwa cewa ya yi: "Kaduna ga alama zata zama ta biyu bayan *Saharanpore* wajen albarkar 'ya'yan itatuwa. Na shuka mangwaro amma cikin shekaru huxu na samu 'ya'yan mangwaro da ban tava ganin haka a Yammacin Afirka ba. "[3]

To, me ya sa Gwamna Lugga yin waxannan bincike? Na farko, wataqila ya samu tarihin varkewar annobar ciwo a tsohon garin Barnawa wadda ta tarwatsa shi. Saboda haka sai ya turo sojijin WAFF don su binciki lafiyar wannan waje, su kuma zama zakarun gwajin-dafi. Na biyu kuma shi ne niyyarsa ta maida Kaduna mai hedkwatoci biyu saboda haka sai ya yi kulaficin bincike da zai nuna lafiya da dacewar wannan waje.

Garin Kaduna ya taso da baqin jini, da farko dai tun 'yar tangarxar da aka samu wajen kafa garin, wannan gari ya sha suka da yawa. An yi ta xauki ba daxi tsakanin Gwamna Lugga da Sarakuna da qyar ya samo kansu, sannan suka ba shi goyon bayan kafa garin, don sun hangi kada garin ya girma ya bunqasa ya fi garuruwan Sarakunan yanka. Amma duk da haka a hankali sai kwarjinin Kaduna ke qara bayyana, kullum sai Gwamna Lugga ke qara sonsa, yaci gaba da tsarinsa mai kyau.

---

1 NAK, SNP 7 4087: 31/7/1913

2 *Ibid.*

3 *Ibid*

Aikin Gina Kaduna

Duk lokacin da aka yi maganar aiki, sai gaban lebura ya faxi, domin shi ne ya san wuyar aiki. An gama aikin shimfixa hanyar jirgi wato Baro zuwa Kano ke nan, sai ga kuma maganar gina sabuwar hedkwata ta vullo. Saboda haka sai dubban leburorin da suke zaune a Dungurun suka shiga shirye-shiryen tasowa zuwa wajen aikace-aikacen sabuwar hedkwata. Idan magana ta aiki ce, to, leburorin ne kan gaba.

Wajen leburorin aiki kuwa, sai qara bankowa suke yi a hankali, saboda akwai albashin leburanci mai tsoka a aikin sabuwar hedkwatar. Saboda yawan leburorin da aka samu, sai aka raba su rukuni-rukuni qarqashin helumomi. Helumomin kuma suna qarqashin Sarkin Alaro. Ta waxannan rukunnai da aka kafa, sai aiki ya rarrabu. Birkiloli aikinsu daban, ga kuma 'yan xibo yashi da kwavar suminti, 'yan xauko bulo da dai sauransu.

Rukunin farko da suka fara tasowa zuwa aikin Kaduna Sabuwar Hedkwata cikin farkon shekarar 1912, su ne Turawa da Injiniyoyin aikin da 'yan safiyo da ma'aikata da rundunar leburori qarqashin Sarkin Alaro Malam Isa. Dukkansu sun sauka a bakin kogi kusa da gadar jirgi. A wannan waje an yi masu 'yan bukkokin zana da xakunan kara. An yi xan qaramin xakin shan magani don kulawa da ma'aikata da leburori, waxanda kashi ashirin daga cikin kashi xari suna fama da zazzavi ko ciwon kurkunu.

Saukarsu a nan ke da wuya, sai suka duqufa aiki wurjanjan. 'Yan sarar itatuwan doka suka shiga aiki, birkiloli da sauran ma'aikata duk su masuka kama ayyukansu. A hankali sai qarin leburori ake ta samu, galibinsu daga qasashen Kano da Zariya, don samun leburori daga waxannan qasashen, ya fi sauqi saboda zirga-zirgar jirgi. An kuma samu Zabarmawa masu yawa.

A cikin farkon shekarar 1912 da aka kama aiki, sai Turawa suka aika zuwa qasar Gwalkwas (Ghana), don samun ma'aikata, wato "artisans " guda xari don su zo su taimaka a rugungunta a gama aikin wannan sabuwar hedkwata. 'Yan buga qonannen tubali da bulon suminti su masun duqufa wajen aiki qwarai da gaske.

Amma saboda a himmatu wajen buga bulo, don kuma a jawo birkiloli zuwa Kaduna don yin wannan aiki sai Mista A.C. Ridsdale, daraktan Fidaburdi ya yi qarin kuxi. Kuxin kowane tubali dubu xaya (1000), sai ya tashi daga fam xaya (£1.00) zuwa fam xaya da sulai huxu (1:4: Od). Amfani da tubali qonanne wajen gina gidaje ya fi, dacewa saboda bulon suminti yana da riqe zafi sosai.

Wajen ma'aikatan gina bulon suminti su ma sun duqufa a bakin kogi, suna kwaso yashi suna tarawa a gavar kogin. Akwai kuma injin fasa dutse da na buga bulo, duk ana amfani da su don aiki ya ci gaba sosai. Cikin xan lokaci kaxan aiki ya yi nisa.

Don a qara himmatuwa wajen aikin wannan sabuwar hedkwata, sai Gwamna Lugga ya buqaci duk shugabannin ayyukan da su riqa aika masa da rahoton aiki a

kowane wata. Su sanar da shi yadda aiki ke gudana da bayanin kuxin da aka kashe da yadda aka kashe su. Waxannan shugabanni kuwa su ne: Mista A.C. Ridsdale, daraktan Fidaburdi da Mista F.G. Pratt babban injiniyan gine-gine.

Saboda a samu tsarin aikace-aikace, sai aka naxa 'yan kwamitin tsarin aikin Kaduna sabuwar hedkwata. Su za su zayyana yadda za a fitar da layuka da kuma gine-ginen cikin tsari. 'yan wannan kwamiti kuwa su ne: Mista C.L. Temple, Muqaddashin Gwamna da Mista Eaglesome, daraktan Aikin Jirgi da Ayyuka da kuma Dr. Blair, babban jami'in kula da Tsabta.

'Yan wannan kwamiti sun yi taronsu na farko a ranar 28 ga watan Fabrairu na shekarar 1914, don su tattauna yadda za a gina gidaje daban-daban a cikin wannan hedkwatar, kuma gidajen ma'aikata su dace da muqamansu. A wannan zaman, 'yan kwamitin sun tattauna kan irin gidajen da ya kamata a gina wa jama'a, misali gidan sama hawa xaya ne ya kamata ko kuma a gina gidan qasa tanqasheshe?

A wannan lokaci an yarda a gina gidajen manyan ma'aikata masu albashin fam xari bakwai (700) zuwa fam dubu (1000) a shekara, kamar su; manyan Shugabanni da Sakatarori da Kwamandoji da manyan Likitoci. Gidajen waxannan manyan mutane a yi shi babba, kuma kowane magidanci ya mallaki gida xaya. Shi wannan babban gida ya qunshi xakin boyi-boyi kusa da shi. Sannan kuma a yi masa babban wajen dafa abinci da wajen bahaya. Irin dai gidajen nan da suke a unguwar Turawa a yanzu. Manyan akawuna masu albashin fam xari biyar (500) zuwa fam xari bakwai (700) a shekara kuwa, gidajensu ya fi na qananan akawuna masu albashin fam xari uku (300) zuwa fam xari hudu (400) a shekara.[1]

Su kuma waxannan qananan akawuna, gidajensu sun fi na sauran jama'ar gari. A taqaice dai, kada a dai-daita ma'aikata ta wajen muhalli. Muhallin kowane ma'aikaci ya dace da muqaminsa. Waxanda suka shaida wannan abin da aka zartar wajen wannan taro na 'yan kwamitin tsarin gina Kaduna kuwa, su ne Mista A.C. Ridsdale da Mista Collard, daraktan Safiyo da Mista Asborne.

'yan wannan kwamitin, sun sake zama na biyu a ranar 1 ga watan Maris. A wannan zama na su, sun ba da umarni a shuka itatuwa a kowane layi da kuma inda za a gina gidan waqafi wato kurkuku. Saboda haka wannan umarni ne ma ya sa aka shuka mangwarori da sauran itatuwa iri-iri a kowane layi. Wannan abu kuwa ya qara wa garin kyau sosai. gwamnatin Ingila ta amince da duk shawarwarin da 'yan kwamiti suka bayar, har ma ta qara ba su waxansu shawarwarin, a cikin wata amsar wasiqa da ta aiko:

Titin Downing
14 ga Afrilu 1914

[1] Duba Fayil na Xakin bincike na Qasa a Kaduna mai lamba SNP – 9/2288/1914

Yallavai (Sir),

Da daraja na amsa wasiqar da ka aiko mai lamba 230 ta ran II ga Maris, ina kuma shaida maka da qara tabbatar maka ta talagram da na aiko na ran II ga watan Afrilu, cewa na amince da shawarwarin da aka bayar a kan gina sabuwar hedkwatar Nijeriya.

A kan maganar gidajen ofisoshi kuwa, na yarda da rahoton 'yan kwamiti wanda ke cikin wannan saqo, cewa kowane Jami'i (banda qananan ma'aikatan relwe) da suka samu gida. Ina mai la'akari da son ganin kowane Jami'i magidanci ya sami masaukin da zai isheshi da iyalansa. Amma kamar yadda nake ji, gida mai xaki guda zai ishi magidanci in an qara masa wani qaramin gyare-gyare. Amma waccan dokar da magabata na suka shimfixa ta cewa ofisoshi masu aure, tilas su biya kuxin masaukin matansu, mai yiwuwa a sake duba ta.

A kan batun tsarin unguwanni da ka aiko a saqo na yarda da duk abubuwan da 'yan kwamiti suka zartar. Amma idan gida mai daraja ta uku "Type C " (gidan Jami'i mai albashin fam 400 – zuwa fam 500 a shekara) ya fi gida mai daraja "Type D " (gidan Jami'i mai albashin fam 300 zuwa fam 400 a shekara) da fifiko mai yawa. Ana iya gina gidaje masu darajar "Type C " ga duk ajin waxannan ofisoshi. Qarin kuxin fam 30 ne akan kowane gida. Haka kuma batun qananan gidaje wato "flat, " masu runfuna ko gidajen sama batu ne da ya kamata a sami shawarwari ofisoshin kula da tsabta da ke kula da wannan wuri.

A kan abun da aka lura a sakin layi na biyu na wasiqarka na faxi cewa a dukkan hali ban *xauki* wurin da za a yi asibiti da ya yi tsaxa ba.

Duk wasu bayanai akan gine-gine magana ce ta mazauna wurin. Ina so in ba da shawara da a lura da kada a gina zauren majalisa a farfajiya guda da kotuna saboda za a iya samun cunKwason jama'a 'yan qasa, amma sakatariya kuwa wadda na fahimci tana cikin wannan shiri ta qunshi ofisoshin lardunan Arewa da na gwamnati.

Na ji wajen da aka nuna a wannan tsari zai isa a yi duk gine-ginen da za a buqata nan da 'yan shekaru masu zuwa. Ina mai farin ciki in ji inda aka sa gaba wajen bunqasar aiki da kuma lokacin da zai xauka a kammala.

Ina mai baka daraja,

Yallavai,
Na ka mafi biyayya, bara mai qaskantar da kai
C. Harcourt
Sa hannu:

Rukunan Ayyuka

Idan lebura da yaransa suka gama aikin wuni, wato aikin tun safiyar fari daga qarfe huxu na asuba (4:00 am) zuwa Yamma qarfe uku da rabi (3:30 pm), kuxin albashinsu sulai da sisi ne wato kwabo goma sha-takwas (18d) ne a kowace rana.

A cikin wannan kuxi sai su fitar wa da helumansu kamashonsa kwabo xaya. A wannan lokaci kuxin leburancin aikace-aikacen sisi ne. Waxannan kuxi ai albashi ne mai tsoka, wannan ma ya jawo hankalin leburori da yawa zuwa Kaduna neman aiki. Saboda isassun ma'aikata da aka samu, sai shirye-shiryen ayyukan da aka yi niyyar kammalawa a cikin shekarar 1914 zuwa 1915 suka samu ci gaba sosai. An qara himmatuwa don a kammala waxannan ayyuka da ke cikin rukunin farko.

A qarshen watan Agusta, an kashe zunzurutun kuxi har fam dubu biyu da xari biyar da casa'in da takwas da sulai goma sha-biyu (£2,598.12d) a kan kayayyakin aiki kawai. An kuma kashe fam dubu biyu da xari bakwai da talatin da xaya da sulai goma sha-shida (£2,731.16d) a kan albashin leburori. Jimilar kuxin da aka kashe domin aikace-aikacen shekarar 1914 zuwa 1915 kuwa, sun kai fam dubu ashirin da biyar da xari huxu da tamanin da biyar (£25,485). Domin qwarewar ma'aikata da leburorin, sai da aka kammala duk ayyukan a cikin qarshen shekarar.

An kammala waxannan ayyuka a rukunin aiki na xaya: Gidajen Turawan soja da gidajen ma'aikata masu sana'o'i da gidajen Akawu da gidan Abasaya da Asibiti. Kafin qarshen watan Satumba kuma, za a gama gina waxannan ayyuka: Gidan Baturen soja da gidajen Turawa da gidajen soja. Ma'aikatar Fidaburdi kuwa an yi waxannan ayyuka: An gina babban sito wanda faxinsa qafa hamsin da tsawonsa qafa xari (100' x 50') ne, 1 sito na tarkace (120' x 50.1') sito na hatsi (60' x 20') da wani na sa tarkace (100' x 100'). An gina ofis mai xakuna uku da kuma kanti mai faxin mita xari (100m).

A qarshen shekarar, an kammala kashi biyu bisa ukun ayyukan da aka duqufa a kansu. A cikin qarshen wannan shekarar na 1914 zuwa 15, akwai masu sana'a har xari biyu da sittin da tara (269), leburori dubu biyu da xari biyu (2,200) da birkiloli arba'in (40).[1]

Daga shekarar 1912, leburori suka fara biyan kuxin haraji, suna biyan 30d (kwabo talatin). Amma cikin shekarar 1915, Mista *M. Porch* Di'o ya faxi qarin haraji na kwabo goma (10d). Kowane lebura sai ya biya kwabo *arba'in* (40d) maimakon 30d na kuxin haraji. Mista *Porch* ya bayyana cewa kowane lebura in zai biya harajinsa, to, ya biya ta hannun helumansa, ko kuma ta hannun waxanda hukuma ta naxa su karva. Baturen ya yi hani ga leburori da kada su riqa biya ta hannun Turawan aiki don gudun kada 'yar tangarxa ta auku tsakanin su da Sarakuna game da kuxin haraji.

A wannan lokaci, idan lebura zai biya kuxin haraji, sai a cire masa 10d a kuxin albashinsa na mako a kuma rubuta, in ya kammala biya, wato bayan sati huxu sai a yanka masa rasixi. Wannan qarin 10d da aka yi, sai ya gallabi leburori qwarai da gaske. Kuxin leburanci a kowane mako 30d, wato aikin 4d a kullum.[2]

---

[1] NAK/4623/1914

[2] *Ibid.*

Leburori na gunagunin wannan qarin kuxi, suna cewa bai kamata ba, sai ga masu karvar kuxin haraji sun iso wajen biyan leburori, suna mazurai, suna jira da zarar lebura ya karvi 30d kafin ya soke a aljihunsa sai su yi wuf su karve 10d. Ganin su ke da wuya, sai duk wajen ya hargitse, hayaniya ta tashi, waxanda suka karvi nasu albashin suka sulale. Domin kada wannan abu ya jawo rikici, sai Mista *Pratt*, babban injiniyan gine-gine ya tsawata wa masu karvar kuxin harajin, ya kuma ce da su, su bar wajen, domin qura ta lafa.

Wannan xan hargitsi ya jawo cikas wajen aiki, leburori sun yi zargin cewa masu karvar haraji na nuna son kai, don waxansu daga cikinsu ba a tambayar su ballantana masu biya. Hasali ma dai da yawa daga cikin leburorin ba su daxe da kama aiki ba. Saboda haka leburori sai suka tarwatse, babu mai zuwa wajen aikin.

Ganin aukuwar wannan abu, sai Mista *E. Illioyd Williams* na ma'aikatar Firdaburdi ya aika wa Di'o, Mista Porch da abin da ya faru, kuma da matakin da leburori suka xauka. Ya ci gaba da bayyana masa, cewa bai ga alamar karvar 40d daga hannun leburan da albashinsa a mako 30d ne, zai taimaka wajen gama aiki ba, don haka ya buqaci Di'o da ya dubi wannan al'amari, ya yi wani abu a kai.[1]

Duk da wannan tunzuri da leburori suka yi a cikin watan Agusta, daga baya aiki ya tafi sosai kamar yadda ake so, har ma an kusan gama ayyukan da aka shirya yi kafin qarshen shekarar 1915. Qarin kuxin haraji bai yiwu ba. An yi manya-manyan gidajen jama'a guda takwas da gidajen jami'ai masu daraja ta biyu guda da gidajen tsarin Ingilishi masu daraja ta uku da ta masu daraja ta huxu guda takwas, a jere, uku na ciki da falo guda talatin na WAFF, wato Unguwar Sojojin Afirka ta Yamma.

Rukunin waxannan shirye-shiryen ayyuka an fara su ne a cikin farkon shekarar 1916. Don a kammala ayyukan wannan shirye-shirye, za a kashe kuxi fam dubu goma (£10,000) da aka riga aka tanada. A cikin waxannan ayyukan rukuni na biyu, za a yi:-

> *Gidaje masu daraja ta uku Gidaje masu daraja ta biyu gidaje shida na masu daraja ta uku 6, da gida guda na mai daraja ta biyu da Gidaje masu daraja ta xaya, da 270 Quarters - 27 blocks W.A.F.F. da ke xauke xakuna xari uku, a barikin Sojojin WAFF (300 blocks in all); da 4 blocks xakuna goma sha-shida a barikin Akawuna, da Gidajen akawuna da Kwalbatoci goma sha-xaya.*

Da dai sauran ayyuka masu dama, su waxannan rukunin ayyukan an kammala su a cikin tsakiyar watan Afrilu na shekarar 1916. Bayan da aka kammala rukunin ayyuka na biyu, sai a ranar 4 ga watan Yuni na shekarar 1916, Mai girma

[1] NAK/869/2787/1915

Gwamna tare da Mista *Eaglesome* suka zauna domin su tsara shirye-shiryen rukunin ayyuka na uku. A cikin wannan rukunin ayyuka ana so a yi:-

> *1st class house, 1 class II houses, 3 class III houses domin sojoji sannan kuma 3-class IV houses domin farar hula, 5 class III houses domin farar hula; da 4 mataimakin manyan akawuna, 161st class houses (8 blocks) 28 2nd class clerk houses (7 blocks), 20 Artisans houses 16 warders houses; da 2 blocks prisons with cook house, laterine, wash place; da Culverts and drainages; da WAFF Line wato layin sojan WAFF; da Up-keep road laterine and Salga etc.*

Saboda haka sai nan da nan ma'aikata da leburori suka duqufa don su gama waxannan ayyukan, kuma cikin xan lokaci kaxan duk an gama su. Gidajen farar hula da aka gina su, ana nufin farar hula masu manyan muqamai waxanda suke aiki tare da Turawan ne.

Ayyukan da suka rage kafin a tare a wannan sabuwar hedkwata kuwa su ne:- Ofishin 'yan Sanda, Kotun Majistare, Masaukin baqi, Asibiti, Ofisoshin ma'aikata, Gidajen Kwana da sauransu. Su waxannan ayyuka da suka saura, an qiyasta za a kashe kuxi fam dubu ashirin (£20,000) don gamasu. Ayyukan da aka kammala gininsu har ya zuwa qarshen shekarar 1916, sun ci kuxi fam dubu xari da goma sha-shida da xari xaya da hamsin (£116,150.00).

An yi ayyuka masu yawa da kyau da inganci, an kuma gina wannan hedkwata da tsari mai qayatarwa. Saboda Lugga nada burin maida Kaduna hedkwatar Nijeriya. Yana da wannan niyyar ne sai maganar kafa hedkwatoci biyu a Kaduna ta taso.

Shirin Kafa Tagwayen Hedkwatoci

Kaduna gari ne da Mai girma Sir Frederick Lugard (daga baya ya zama Lord Lugard) ya kafa, ya kuma qawatar da shi domin ya zama hedkwatar Nijeriya baki xaya. Wannan qasaitaccen bature, kuma gwani a sha'anin mulki, shi ne Gwamna na farko a Nijeriya ta Arewa. Ikko da kudancin Nijeriya na da Gwamnoninsu kafin a haxe su a shekarar 1906. A wannan shekarar ce Gwamna Lugga ya tafi qasar *Hong Kong*, kafin Sakataren Mulki ya maidoshi Arewa a shekarar 1911, inda ya haxa qasashen Arewaci da kudancin wannan qasa domin ta zama haxaxxiyar qasa sai suna Nijeriya a shekarar 1914.

Kamar yadda aka yi bayani ne wannan abu, wato kafa qasar Nijeriya ya yi wa neman samun wajen da ya dace da hedkwata a Arewa qaimi sosai. Amma ba samun waje kawai Lugga ke tunani ba, a'a wannan waje da aka samu a Kaduna ya so ya kafa hedkwatoci guda biyu ne: xaya hedkwatar Nijeriya, niyyarsa ya maida garin Kaduna hedkwatar Nijeriya, xaya kuma wato garin Barnawa ta zama

hedkwatar Arewa, Kaduna sai ya zama gari mai tagwayen hedkwatoci ke nan. Har ma ya yi tunanin yadda za a yi da gine-ginen gwamnati da ke Ikko bayan, an maida Kaduna hedkwatar Nijeriya. Gwamna Lugga ya qara jaddada wannan niyya tasa, a rahotonsa na Haxaxxiyar Qasa wato *Amalgamation Report*, inda ya ce: "Gidan Gwamna da ke Ikko zai zama qasaitaccen otal, in qoqarin mai da tushen mulki garin Kaduna ya cimma nasara. "[1]

Wannan bayani ya tayar wa da 'yan Kudu hankali sosai. Saboda su mutane ne masu kishi da hangen nesa don haka sai suka ga tashin Ikko daga matsayin hedkwata babbar asara ce gare su baki xaya. Kaga wato tun Nijeriya ba ta kai ga shekara guda ba 'yan Kudu sun fara nuna kishi da bambanci wajen duk wasu abubuwan da za su kawo ci gabansu. Ai kamata ya yi su rungumi wannan shiri na maida Kaduna hedkwatar Nijeriya, saboda an zavi garinne bisa dacewa, ba bisa son rai ko kuma qabilanci ba. Amma maimakon haka sai 'yan Kudu suka yi wa shirin rina. Suka tashi haiqan wajen ganin shirin yaci tura.

Turawan mulki da yawa sun goyi bayan wannan shiri na Gwamna Lugga, na maida Kaduna Hedkwata biyu saboda sun ce garin Ikko bai dace da zama hedkwata ba domin ba ya tsakiyar qasa, kamar yadda tsarin kafa hedkwatar qasa ke buqata. Amma duk da haka sai 'yan Kudu suka yi ta yin maqarqashiyar rusa wannan shiri, suna kuma amfani da qungiyoyi da kafafen watsa labarai, suna sukar wannan shiri da kakkausar harshe inda suke kuma nuni da dacewar Ikko. Hankalinsu ya qara tashi da ganin an shimfixa hanyar jirgi da ya haxa garin Fatakwal da Kaduna. Sun kuma fassara yin wannan hanyar da wani yunquri ne na dakushe Ikko ta kawar da jigilar kayayyakin Arewa da za a kai qetare daga gareta.[2] Wannan 'ya nuna tun ran gini tun ran zane, 'yan Kudu ba su tashi da imani da Nijeriya qasa xaya ce mai al'umma xaya ba. Sun tashi ne da so da kishin yankunansu.

Duk da qorafe-qorafe da 'yan Kudu suke yi, Gwamna Lugga ko gezau bai yi ba. A shekarar 1913 lokacin da haxa Nijeriya ya zama zahiri, amma Gwamna bai tayar da maganar xauke hedkwata daga Ikko ba. Saboda haka sai Sakataren Mulki L. Harcourt ya tuntuve shi akan batun, inda ya rubuto masa da cewa:

"Da farko dai ina son ka wayar da ni kan wannan shiri na kafa hedkwata a tsakiyar qasa, ita wannan hedkwata ce ta Nijeriya ta Arewa. Na fahimci da farko kana son kafa hedkwatoci biyu ne da suke kusa da juna amma ba a haxe ba. Daga bisani kuma sai ka qara jaddada maganar wani qaramin waje a tsakiyar qasa, ba tare da maganar hedkwatar Arewa ba. Wannan bayani yana da amfani musamman idan aka yi la'akari da babu isasshiyar qasa a Barnawa (wajen da

---

1 *Lugard and the Amalgamation of Nigeria*, London, 1968

2 A.K Medugbon, Kaduna, Nigeria, shafi na 25

kake so) da kafa gururuwa guda biyu ko kuma babban gari xaya. Ina farin cikin sanin ra'ayoyin ka akan wannan batu da kuma dalilan ka. Zan qara da cewa, ni na a yanzu ina da goyon bayan ra'ayin kafa hedkwatoci biyu a gari guda.[1] "

Akwai gagarumin shirin mai da Kaduna hedkwatar Nijeriya; a cikin wannan shirin za a yi amfani da Ikko ne a lokaci lokaci. Varkewar Yaqin Duniya na farko ya kawo wani babban tarnaqi wajen aiwatar da wannan shiri saboda rashin samun isassun kuxi, abin da ya tilasta Lugga taqaita kashe kuxaxe wajen gina Kaduna. A kasafin kuxin da Gwamna ya gabatar da farko an qiyasce za a kashe fam dubu xari biyu da tamanin da hamsin da biyu (£280,052) a qarqashin sashe ashirin da biyu wato "22 Departments " da za su kula da gina garin Kaduna. Waxannan sashen, ko tsangayu wato *Departments*, sun haxa da na: *Governor*, *Cantonment*, *Secretariat*, *Political Administration*, *Legal and Judicial*, *Treasury, P&T, Audit, Printing, WAFF, Battalion Headquarters, Companies, General, Police Headquarters, Detachment, Prisons, Forestry and Agriculture, Medical Sanitation, Education, Surveys and Mines, Transports and PWD.*[2]

Dalili na biyu da ya shafi gagarumin shirin shi ne tsawon lokacin da kwalekwalen kai saqo wato *Mail Boat* ke xauka kafin ya isa Ikko. Ofishin Sakataren Mulki qarqashin Milner ya qi karvar wannan shiri saboda ba shi buqatar aiwatarwa da gaggawa. An yi nuni da cewa tafiya daga Kaduna zuwa gavar teku, na xaukar tsawon kwanaki biyu. Wato kaiwa da karvowar saqo daga Gwamna zai xauki lokaci mai tsawo. Dalilin haka zai sa jiran zuwan kwalekwalen kai saqo daga Ikko har na tsawon lokaci. Jiran jirgi har na tsawon sati biyu abu ne da ba za a jure masa ba.

Dalilin haka ya sa Walter H. Long, ya umarci Lugga a wasiqar da ya aika ma sa ta ranar goma ga watan Maris na shekarar 1918 inda ya ce, "Ofisoshi da ma'aikatu da ke Dungurun ne kawai za su taso zuwa Kaduna amma banda waxanda suke zaune a Ikko. "[3] Amma tun a watan Oktoba na shekarar 1917 Sakataren Mulki na wannan lokaci Mista Bona Law ya ba da wannan umarnin cewa ofisoshin da ma'aikatun da ke Dungurun ne za su taso zuwa Kaduna, banda waxanda suke zaune a Ikko. Ya kuma umarci Gwamna Janar da ya rage kashe kuxi a Kaduna.[4] Duk da haka an ci gaba da gine-gine har ma a qarshen shekarar 1919 an samu yin wasu manyanyan gine-gine kamar gina Majalisar dokoki da

---

1 NAK/SNP/15/191: *Letter from L. Harcourt to F. Lugard*, 13/6/1913

2 E.O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na . 154-155

3 NAK, SNP 15, 56/1918; *Kaduna Capital: Restiction of Expenditure during the war*.

4 *Ibid*. 8/4 2/1917.

gidan gwamnati da ke wajen gidan Shawara a yanzu. Ana wata ga wata nan. Gwamna Lugga ya bar Nijeriya.

Sir Hugh Clifford, wanda ya gaji Gwamna Lugga a matsayin Gwamna Janar na Nijeriya daga shekarar 1919 zuwa 1925 bai amincewa shirin da ya gada daga Lugga ba. A nasa ra'ayi ya kamata hedkwatar mulki ta zama jagora ga shirin haxaxxiyar qasa, saboda haka ya ba da shawara da cewa tunda Ikko ita ce cibiyar kasuwanci mafi girma da harkokin siyasa da zaman jama'a tare da wayewa, da ta ci gaba da zama hedkwatar Nijeriya har na wasu tsawon shekaru masu zuwa.[1] Shi Gwamna Clifford, ya yi amfani ne da hujjojin tattalin arziqi wajen barin Ikko da ta ci gaba da zama hedkwata, musamman idan aka yi la'akari da matsayin wannan garin na babbar tashar jirgin ruwa wanda ba kamarsa a Nijeriya.

Maganar wannan gagarumin shiri na maida Kaduna hekwatar Nijeriya, ta sa ke tasowa bayan yaqin duniya na biyu. A wannan lokaci Gwamna Janar *Sir Arthur Richards* ya yi yunqurin taso da hedkwatar Nijeriya daga Ikko zuwa Kaduna. Saboda haka sai ya buqaci a binciko nawa ne wannan shiri zai ci. An qiyasce za a qashe zunzurutun kuxi fiye da fam miliyan guda (£1,000,000) wajen taso da tushen mulki da manyan ma'aikatu zuwa Kaduna. Idan aka yi la'akari da yadda ofishin Sakataren Mulki ya tsuke bakin aljahu waxannan maqudan kuxi ya wuce abin da gwamnati za ta iya kashewa a wannan lokaci. Dalilin haka ya sa maganar ta sake kwantawa.

An kuma qara taso da ita a shekarar 1954 a lokacin Taron London wato London Constitutional Conference, amma sai aka ba da hanzarin rashin issasun kuxi da za a aiwatar da shirin. Mista Oliver Lyttleton, Sakataren Mulki wanda ya shugabanci tarukan London da aka yi shekarar 1953 da 1954, ya faxi cewa: "Ana yawan assasa tsadar kuxi wajen gardama akan batun tayar da hedkwata. "[2] Dalilin rashin isassun kuxi ya sa aka tashi wannan taro, da a bar Ikko ta ci gaba da zama hedkwata har tsawon wani lokaci. Duk da haka an ci gaba da yawan qorafe-qorafe da ke nuna rashin dacewar Ikko.

An sha yin taqaddama akan matsayin Ikko, a matsayinta na Tarayya da kuma matsayinta na mallakar Jihar Yamma. Babbar rigima ta tashi, game da yadda Ikko za ta zama zuwa gaba. Sardauna ya ce, "a lokacin tana cikin sashen Jihar Yamma ne. Action Group suka fa dage cincin-qarfinsu, baki na yi, hannuwa na yi, tun ma ba da bakin ba, sai ji ka ke va va va va! Sauran kuma (har da mu ke nan) sai muka dage, kai da fata amma don wani mugun nufi ba, muka ce lallai sai Ikko ta yi zaman kanta.[3]

---

1 E.O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na 157.

2 Ahmadu Bello, *Rayuta*, shafi na .....

3 *Ibid*., shafi na 172.

Amma daga qarshe, da sanya bakin gwamnatin Ingila sai aka dai-daita shawara akan al'amarin, aka bar yankin qasar Ikko ya zama na Tarayya, ya daina zama qarqashin Jihar Yamma.[1] Babu Jihar da ta fi Jihar sanin amfanin Ikko wajen bunqasar tattalin arziqi da na siyasa. Saboda haka ita ce akan gaba wajen ganin shirin maida hedkwatar Nijeriya zuwa Kaduna ya ci tura. Garin Ikko, wani hatsabibin gari ne mai albarka. Ga Kaxan daga cikin abin da Firimiya Sir Ahmadu Bello ya ce, game da Ikko da shirin maida Kaduna hedkwatar Nijeriya:

"Wani bayani na game da tarihi a nan zai yi amfani, idan na faxe shi, domin zai fi fito da komai a fili. Ga yadda tarihin yake: Tsibirin nan na Ikko a cikin shekarar 1841 ne ya koma qarqashin Ingila, amma ba a cewa wurin yana bin Ingila sai dai a ce sashenta ne, don saboda a sami hana cinikin bayi, wanda a lokacin Ikko ita ce hedkwatar cinikin. Bayan 'yan shekaru kaxan kuma wani yankin qasa mai tsawo mil 150 da faxi mil 12 daga kan iyakar mu da Dahomey zuwa Gabas shi ma aka haxa duk da shi. Wata qila a zatona an yi haka ne don a kange tsibirin nan na Ikko daga farmakin yaqi daga ainihin qasar ne. Kuma shi tsororon yankin nan, ya fi zama sara-sara a Arewacin Ikko, kuma don a sami duba kwaroron nan na wutsiyar teku wanda ya taso tun daga Porto Novo ya malala zuwa inda Kogin Neja ya shiga teku, kamar mil xari uku ke nan, wanda zamanin da, kai, har a yanzu ma wuri ne da a ke ciniki qwarai irin na bakin teku.

"Har shekaru casa'in, Turawan lngilishi na riqe da wurin nan, kuma babu ruwan wannan wuri da masu mulki na cikin sauran qasar. A na kiran qasar Colony of Lagos, mutanen da ke cikinta kuwa suna jin sun fi kowa, tun da yake su talakawan Ingila ne tsintsa, fiye da sauran mazaunan qasar. A wannan zamanin, zai zama a hagunce, idan za a ji suna cewa Haka nan, ko kuwa? Cikin shekarar 1914 aka canja sunan qasar, aka sa masa suna Colony of Nigeria, sauran qasar kuwa ana kiransa da Turanci Protectorate of Nigeria, bayan an haxa qasar Nijeriya ta Arewa da ta Kudu. A farko-farkon al'amarin sunan sarautar mai duba qasar Administrator, daga baya aka canja shi ya zama Kwamishina. wanda ke qarqashin gwamnan Nijeriya. Ba ta kuwa tava zama qarqashin mulkin Yarbawa ba da ke Arewacinta, sai da aka kafa tsarin nan na Jiha-jiha, sa'ad da aka yi kuskuren nan da aka sa Ikko cikin Jihar Yamma.

"Tun daga wancan lokacin ne Jihar Yamma ta dage, tana ta neman a bar mata ita ta riqe. Kai, ta kai ma Jihar Yamma sun ce su sun yarda su ba da kuxi, su kuma gina wata sabuwar Hedkwatar Tsakiya (amma ko ta yaya lallai ta kasance cikin Jihar Yamma). An kuwa sha duba wannan shawarwari. Misali, lokacin da Gwamna Lugga ya haxa Arewa da Kudu, sai ya shirya sabon garin nan na Kaduna, don ya zama hedkwatar duk Nijeriya. Amma ga yadda na ji, wai sai

[1] Ahmadu Bello, *Rayuta*, shafi na .....

Ofishin Sakataren Qasashemmu suka ce ba su yarda ba, tun da yake tafiyar kwana biyu ce a jirgi daga teku. Saboda idan suka aiko da saqonsu mai daraja zai daxa kafin ya sadu da Gwamna. Kuma amsoshin da za a bayar, ba za a iya kai su bakin teku cikin lokaci ba, har yadda za a iya sa su cikin jirgin ruwan busta. Ko da yake dai ba safai su kan sami yin Haka nan xin ba.

"Ayya, sai dai Ofishin Sakataren Qasashenmu ne ya yanke wannan maganar. Wahalhalun da za su zo a gaba, da duk an yi maganinsu ke nan. Kaduna da yake tana tsakiyar wurin da babu Kowa, sai daji. Da ita ce ta fi dacewa da a yi Haka nan. Akwai isasshen ruwan sha, akwai isasshen fili da za a iya qara buxawa, sa-an nan ga fili isasshe na yin babban filin jirgin sama. Tashi sama na wurin kamar qafa 2,000 ne daga bakin teku, sa'an nan kuma yanayin qasar mai kyau ne. Hasali dai tana da dukkan abubuwan da lkko ba ta da su, kuma da ba ta sami mummunan mugum abu na lkko ba, wato iskanci, wanda yake shi ne duk mai mutunci bai jure masa.

"An kuma sake duba shawarwari, ina kuwa zato Lord Milverton ne ya sake duba maganar. Sai aka ga in za a taso manyan wuraren aiki, a taso da hedkwata xungum ta gwamnati sai an kashe fam miliyan guda, to, wannan kuwa, qasar nan ba za ta iya shi ba, don jakarta ba ta da nauyi. Babu wanda ya san irin ximbin kuxin ajiyar da ke ta haxaka. Sabuwar asibitimmu ta Kaduna kafin a gama ta sai an kashe fam miliyan biyu, don haka kafa hedkwatar da kuxinta ba su kai yana asibitin nan ba, bai kyautu a ce ta yi tsada ba.

"Hasali ma dai a taron nan na London, Mr. Lyttelton ya ce, "Ni a ganina, game da gardamar da a ke yi cewa tsada ita ce za ta hana a ta da hedkwata, wannan kururuwa ce fiye da kima. "

"Al'amarin babba ne gare mu, domin kuwa a cikin yankin qasar nan na Ikko akwai tashar jiragen ruwan nan, Apapa, daga qetaren gava, to, ta nan ne kuwa duk galibin kayan cinikinmu, waxanda muka sayo, da waxanda muka sayar, suke biyowa. Gaskiya ne kam kaya da dama a kan sauke su a Fatakwal, amma dai mafi yawa sun fi bi ta Apapa. Wanda kuwa duk ya sami riqe Ikko, to, shi ke riqe da Apapa ke nan, don haka yana iya toshe mana hanyar ciniki. Bisa ga yadda al'amarin zumuntarmu ya kai da Action Group a lokacin, (haka kuwa yake har kwanan gobe) sai muka riqa ji a rayukanmu cewa hankalinmu zai fi kwantawa idan wannan wuri aka bar shi a hannun gwamnatin Tarayya, wadda a cikin waxansu harkokinta muna iya tsoma bakimmu; ko da yake ba mu ke riqe da gwamnati ba, fiye da idan waxansu ne ke riqe da al'amarin. "[1]

An daxe ana nuna cewa cire hedkwatar qasa daga Ikko zai taimaka gaya wajen raba arziqin qasa ga duk sassan Nijeriya. Idan hakan ba zai yi wu ba, to,

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na . 172-174

ana iya barin Ikko da ta zama cibiyar kasuwanci. Amma sai a shekarar 1976 ne gwamnatin Mulkin Soja ta Janar Murtala Ramat Mohammed ta aiwatar da umarnin da kwamitin Aguda ya bada ta a maida hekwatar Nijeriya Abuja dake tsakiyar Nijeriya. A wannan shekara ce aka cimma burin Gwamna Lugga na taso da hedkwata zuwa tsakiyar Nijeriya.

A babban shirin mai da hedkwatar Nijeriya a tsakiyar qasa. Gwamna Lugga ya so ya kafa hedkwatoci biyu maqwabtan juna: xaya a Kaduna, xaya kuma a garin Barnawa. Barnawa wani gari ne da Fulani suka kafa wanda ya yi suna a lokacin zuwan Barebari. Garin ya zama wani babban cibiyar Addinin musulunci a lardin Zazzau. Wannan gari yana Kudu mas- Gabas da kogin Kaduna daga gadar jirgi. Gwamna Lugga ya so ya maida wannan gari hedkwatar Arewa, garin Kaduna kuma ya maida shi hedkwatar Nijeriya.

Wata qila Gwamna Lugga ya samu labarin varkewar annobar ciwon makanta, a tsohon garin Barnawa ne wanda ya sa jama'ar garin suka yi qaura zuwa sabon waje, a inda garin yake yanzu. A shekarar 1913 gwamnan Lugga ya tura rundunar sojan WAFF da zuwa wannan gari don su zama zakarun gwajin dafi. Amma babu wani ciwo da a ka ce ya vullo. Haka kuma saboda wannan shiri ne, Gwamna Lugga ke zuwa garin Barnawa akai-akai. Ya kan hau jirgi ya tsallako da shi daga lambun gwamnati, wanda kogin Kaduna ne ya raba shi da Barnawa. A wannan lokaci sai ya kai ya komo, saboda son ya aiwatar da shirinsa na maida Barnawa hedkwatar Nijeriya ta Arewa.

Wannan shiri na kafa tagwayen hedkwatoci ya samu amincewar gwamnatin Ingila, wannan ya sa Sakataren Mulki Mista L. Harcourt ya rubotawa Gwamna Lugga wasiqa ta musamman don ta qara masa qaimi wajen ci gaba da wannan muhimmin shiri na gina tagwayen hedkwatoci a wannan waje mai albarka. Ko da yake al'amura sun taso daga baya, sun tilasta gwamnan barin wannan gagarumin shiri, amma Clifford magajinsa bai ji daxin haka ba; ya kushe barin Ikko ta ci gaba da zama hedkwata. Alal misali, a shekarar 1919 ya yi tur da sakatariyal Ikko da ya ce ta cika cunKwaso.

Gwamna Lugga na da hujjoji masu qwari wajen sonsa na xauke hedkwata daga Ikko zuwa Kaduna. Babu son rai a wannan zaven da ya yi. Ya yi matuqar imani da cewa Kaduna ta fi dacewa da zama hedkwatar Nijeriya saboda tana da yanayi mai kyau, da isasshiyar qasa mai faxi. Kaduna na iya zama garin tushen mulki fiye da Ikko, idan xauke hedkwata daga Ikko bai samu ba, to, ana iya kafa hedkwatocin Nijeriya guda biyu: Kaduna da Ikko, A kan haka ne. gwamnan ya yi tsokaci da cewa:

"Gwamna Janar ka iya amfani da waxannan hedkwatoci, a inda a kowace hedkwata yana da gida. Saboda haka yana iya zama a kowannensu a lokaci – lokaci. Daga hedkwatar da ke tsaqiyar qasar, zai samu sauqi da shi da manyan

shugabanninsu, su riqa ziyarar Kudu da Gabas ko Yammacin wannan qasa ta hanyar jirgi. Daga hedkwatar da ke Kudu kuma yana iya ziyarar ta hanyar jirgin Baro, ko kuma takan kogin Kwara duk haka kuma yana kusa da Arewa. Ikko kuma sai ta ci gaba da zama a matsayin cibiyar kasuwanci. " [1]

A wannan bayani Gwamna Lugga ya nuna a fili ya ce kafa tagwayen hedkwatoci ba a Arewa ba, a Nijeriya baki xaya shi ne mafi dacewa. A wannan shiri sai garin Kaduna ya zama hedkwatar mulkin qasa saboda dacewarta a tsakiyar Nijeriya. Ikko kuma sai ta zama hedkwatar kasuwanci saboda ta na da babbar tashar jirgin ruwa. Ko shakka babu wannan shiri zai kawo wa Nijeriya ci gaba ta kowace hanya. A wannan qasaitaccen shiri, ana so Nijeriya ta sami tagwayen hedkwatoci biyu Kaduna da Ikko. A Kaduna kuma a samu tagwayen hedkwatoci, garin Barnawa ya zama hedkwatar Arewa, Kaduna kuma hedkwatar mulki ta qasa baki xaya. Kogin Kaduna ne kawai zai raba su. Amma rashin cin nasarar wannan shiri ya kawo cikas ga ci gaban Nijeriya baki xaya. Dalili kuwa zunzurutun kuxaxen da aka kashe wajen maida Ikko ta dace da zama hedkwata, musamman wajen cike rafuka da tafkuna da zaizayar qasa da ambaliyar teku ke kawowa a kowane lokaci, sun isa a bunqasa garuruwa masu yawa a Nijeriya.

Amma saboda da dagewar da 'yan Kudu suka nuna da kutingwiloli iri-iri da suka kafa sun taru sun hana kaiwa ga nasara. Garin Kaduna bai sami kaiwa ga muqamin da Gwamna Lugga ya nufe shi da shi ba. Zaman hedkwatar qasa a Ikko ya ci gaba da tauye ci gaban sauran wurare a Nijeriya daga shekarar 1914 har ya zuwa shekarar 1976. Duk da qorafe-qorafe da jama'a ke yi akan rashin dacewar Ikko a matsayin hedkwatar Nijeriya. A duk tsawon shekaru sittin da biyu an cunkusa 'yan Nijeriya a Ikko ba kuma yadda za su yi, sai a zamanin mulkin shugaban qasa Janar Murtala Muhammed wanda a ran 3 ga Fabrairun shekarar 1976, ya ba da umarnin a maida hedkwatar Nijeriya zuwa Abuja tsakiyar Nijeriya. Wannan sabuwar hedkwata tana da nisan kusan mil xari da hamsin Kudu da garin Kaduna. An kafa hedkwatar ce bisa dacewa a kan hujjoji masu qwari sosai. Turawan Mulki waxanda suka shimfixa harsashin ci gaban qasa, su ne su ka kuma kafa garin Kaduna sun kuma ba da hujjojinsu bisa wannan zave.

Dacewar Kaduna

Turawan Mulki sun yi amfani a da hikima da basira wajen zaven wajen da ska kafa Kaduna da kuma qawatar da garin da gine-gine masu kyau da qarko. Gwamna Lugga wanda ya jagoranci wannan muhimmin aiki, ya cancanci yabo sosai. A duk wahalhalun da ya sha wajen neman hedkwata da kuma baqar wahala da shi da jama'arsa suka sha a zaman da suka yi a garin Lakwaja da Jebba da

[1] *Lugard the Amalgamation of Nigeria*, shafi na . 95-96

Dungurun, kafin su yi katari a tsakar jeji, ba su sa shi ya yi zaven waje da zai kawo nadama ba. Akwai dalilai masu yawa da suka sa shi zaven dajin doka wajen kafa hedkwatar Nijeriya, amma mafi amfani a wajenmu a wannan zamani shi ne rashin tayar da wani gari ko qauye. Saboda haka sai aka kafa garin a *Virgin Bush* kamar yadda suka kira dajin Doka.

An kafa wannan gari ne a zamanin Mulkin Mallaka saboda ya zama tilas a kafa hedkwatar mulki a wajen da zai samu kyakkyawan tsaro. Amma a zaven da su ka yiwa Kaduna, tsaro ba shi ne maqasudin kafa garin ba. Don kuwa su 'yan kwamitin da aka danqa alhakkin samo wajen kafa hedkwata, an ba su abubuwan da za su yi la'akari da su, kamar haka:

1. A samu waje da zai dace da:

   a) Kafa hedkwatar Nijeriya ta Arewa.
   b) Kafa hedkwatar Nijeriya a tsakiyar qasar.
   c) A duk waxannan hedkwatoci su zama akwai hanyar jirgi.
2. A samo waje ko wurare a kusa da Dungurun ko Kaduna, inda hanyar jirgi ta qetare kogin Kaduna.
3. A samu tsararriyar hanyar samun ruwa isasshe mai kyau daga kogi.
4. A samu tanqasasshen waje mai faxin qasa mai kyau, da tsabta, da albarkar qasar da ta dace, da shuke-shuken filawa da itatuwa. Wannan waje ya zama ba shi da haxarin tururi haske mai cutarwa wato *radiation* da ke kusa ko nesa da wajen, wanda ka iya gurvata wajen ta hanyar iska ko ta qorama.
5. A samu waje da ba shi da yawan qwari, musamman sauro, da qudan tsando, da qudaje da sauran qwari masu cizo. [1]

'Yan wannan kwamiti waxanda suka haxa da Mista H.R Palmer Kwamishina mai kula da kuxaxen shiga na cikin gida, da Keftin H. Howel da M. Blair babban Jami'i mai kula da tsabta. Xaya daga cikin dalilan da suka sa aka zavi wannan waje, shi ne rashin samun gari ko qauye a cikinsa. Wannan batu da *Medugbon* ya baiwa muhimmanci sosai, saboda haka ne ya ce:

"Xaya daga cikin fa'idojin kafa Kaduna a wannan waje shi ne rashin samun wata qabila a cikinsa. Amma Mazaunai dake kusa da wannan wuri, suna wajen qauyen Kakuri da ke Kudu inda akwai tsirarun gidajen Gbagyi a Kudu maso

[1] NAKSNP91 – *Kaduna Headquarters*

Yamma da Kudu maso Gabashin wannan waje. Duk waxannan wurare su na a qalla mil huxu ne tsakaninsu da hedkwatar gwamnati ."[1]

Wannan shaida ce mai kyau da qarfi da ke nuna babu wata qabila da aka tarwatsa wajen kafa garin Kaduna, ballantana yin haka ya haifar da kishi da qorafe-qorafe a tsakanin mazauna wannan sabuwar hedkwata. Abin da za a qara a nan shi ne ba qabilar Gbagyi ce kawai ke maqwabtaka da dajin Doka ba, akwai wasu garurawa da suka kewaye shi, waxanda suka haxa da: Barnawa da Kinkinau da Maqera. Idan a ka yi Arewa da kogin Kaduna akwai Kurmin Mashi. Haka nan kuma ga garin Kawo a gavar kogin daga Arewa maso Gabashin wannan waje daga gadar jirgi. 'Yan kwamitin Palmer sun jaddada wannan batu, a inda suka rubuta cewa:

Wannan waje yana da fa'idoji masu yawa ta fuskar sojoji da matsayin hedkwatar Nijeriya ta Arewa. An kafa hedkwata a wajen da bai shigo cikin garin Hausawa ba, za a haxa shi da lardin Gabas ta hanyar jirgi. Wata qila a tsakanin waxannan larduna biyu, inda hargitsi ka iya barqewa shi ne lardin Arewa. In banda Zariya, Kaduna ce mafi dacewa da kafa sojoji a shirin ko ta kwana. "[2]

Max Lock, Baturen da ya yi katafaren safiyon Kaduna ya ce Kaduna kamar *Brasilia* take wato gari a tsakar daji. Amma kurmin da ya kewaye *Brasilia* wato *Moto Grosso* ba kamar qasar "Savannah " da ke Nijeriya ta Arewa ba ce, wadda take da albarkar qasa. Duk da haka ba albarkar qasa ce ta sanya zaven wannan waje ba, wanda Lugga ya yi a shekarar 1912. An zavi wannan waje ne saboda dacewarsa da tafiyar da mulki da kafa hedkwatar soji, a Nijeriya ta Arewa wata makekiyar qasa wadda ta fi qasar Faransa girma. Max Lock ya ba da dalilai guda huxu da suka sa a ka kafa garin Kaduna a wannan sabon waje kamar haka:

1. Wajen na da isasshen ruwa daga kogin Kaduna wanda yake hannu ne na kogin Kwara.
2. Kaduna na tsakiyar masarautu goma sha-uku, *Thirteen Emirates* waxanda su ne Nijeriya ta Arewa wato *Protectorate of Northern Nigeria.* A shekarar 1912 aka haxe su don su zama hadaxxiyar qasa Nijeriya.
3. An shimfixa hanyar jirgi a shekarar 1911 wanda ya haxe Ikko da birnin Kano. An kuma shirya ya zama mahaxar hanyar jirgi ta Arewa da Yamma, hanyar ta haxe da ta Fatakwal daga Gabas. Ko da yake ita wannan hanyar da aka xauko ta daga gavar teku a shekarar 1914 ba ta haxe da Kaduna ba

---

[1] A.K Medugbon: *Kaduna, Nigeira*, shafi na 39

[2] Palmer, *Report on Site*, 9

sai a shekarar 1927; a lokacin da aka buxe hanyar jirgi daga Kafanchan zuwa garin Jos. Matsayin wannan gari na mahaxar hanyoyin jiragen qasa Kaduna Jamsin wato *Kaduna Junction*, shi Lugga ya hango saboda muhimmancinsa.

4. Daga qarshe, wannan wajen tushen mulki da cibiyar hedkwatar sojoji na wajen da ke kusa da qasar Gbagyi a tsakiyar lardin Zazzau, amma ba shi da alaqa ta qut-da-qut da wani gari saboda haka garin ba shi da illolin siyasar mallakar wata qabila.[1]

Sabon wajen da aka samu ya dace sosai da kafa hedkwata saboda yana da kyawon yanayi, da qasa mai albarka, da tuddai da qoramu da suka dace da zama da shuke-shuke.

Yanayi Mai Kyau

Yanayi mai kyau ya janyo hankalin Turawan mulki zuwa wannan waje, yana kuma da armashi sosai. A watan Afrilu ake samun faxuwar damina ana kuma samun isasshen ruwan sama har ya zuwa watan Satumba. Da rani a kan sami lokacin hunturu mai sanyi da bujin iska, da ke farawa a qarshen damina har ya zuwa watan Fabrairu. Garin Jos ne ya fi Kaduna kyawon yanayi a Arewa. Amma duk da haka yanayin wannan waje yana da armashi sosai, bai cika zafi ba, ba shi kuma da matsanancin sanyi.

Gwamna Lugga ya cancanci yabo sosai da zaven wannan waje da a kafa hedkwatar Arewa. Domin kuwa dacewar wannan waje ta kowace hanya sai qaruwa take yi a kullum. Don kuwa a yanzu garin ya zama tagomashin gari mai kyawon yanayi wanda ya dace da zaman kowa Turawa da 'yan qasa. Don haka ne Mista K.J Bryant ya ce: "Duk mazauna wannan waje, ma'aikata da 'yan kasuwa su yi godiya ga Gwamna Lugga wajen zaven wannan waje da ya yi don kafa garin Kaduna. "[2] Haka kuma wannan Babban Dio K.J Bryant ya yi nuni da cewa rashin tashin wata qabila don kafa Kaduna abu ne mai fa'ida matuqar gaske.[3] Domin haka ne garin Kaduna ba shi da alaqa da wata qabila da za ta ce an tashe ta don kafa wannan gari.

---

1 Max Lock and Patners, Kaduna: 1917, 1967, 2017; *A survey and Plan of the Capital Territory for the Government of Northern Nigeria*, Faber and Faber Limited 24 Russell Square London (1967), shafi na 19.

2 K.J. Bryant, *A Guide to Kaduna, The Capital of Nigeria, Zaria* (1959), shafi na 2

3 *Ibid.*

Zama da Mallakar Qasa

Medugbon a qulaficin bincikensa akan Kaduna ya faxa, ya kuma nanata wannan batu inda ya ce:

Wani abu mai fa'ida sosai shi ne an kafa Kaduna a wajen da ba wata qabila da ke zaune. Mazaunin jama'a mafi kusa da wannan waje shi ne qauyen Kakuri da ke Kudu da kogi da mazaunan Gbagyi a Kudu maso-Yammaci da Kudu maso Gabashin wannan waje. Duk waxannan mazaunai wato "settlements " suna da nisan aqalla mil huxu da hedkwatar gwamnati.[1]

Abin da Medugbon ya yi nuni da shi, shi ne an kafa gari a wajajen da ba shi da alaqa ta qut da qut da wata qabila. Fa'idar yin haka ita ce Bryant da sauran Turawa su ka yi ta nanatawa a rubuce-rubucensu a kan Kaduna. Zama a wannan waje da mallakar qasar wajen iko ne da Turawa suka ce ya rataya a wuyansu. Dokar da ta mallakawa Turawan Mulki, qasar Arewa ta fara aiki ne daga shekarar 1902, a lokacin da masarautar Ingila ta qarbe ikon mallakar qasa daga Turawan Kamfani. A wannan shekara ce, aka zartar da hukuncin mallaka qasa ga gwamnatin Ingila.[2]

A cikin shekarar 1886 gwamnatin Ingila taba waxansu mutane iznin su zama kamfani su kira kansu *Niger Company*, kuma su yi ciniki a Nigeriya. Kuma an ce lallai su ga an kiyaye doka da oda a wuraren da su ke ciniki. Wannan kamfani ya kafa xakunan shari'a, ya kafa 'yan Sanda, kuma suna karvar haraji. Babban wurin harkar wannan kamfani shi ne Asaba. Haka aka zauna shekaru da dama har ran 1 ga Janairun shekarar 1900, gwamnati ta karvi mulkin Nijeriya ta Arewa ta zama cikin qasashen mulkin Sarkin Ingila.[3]

Ko da yake wannan kamfani ya samu iznin yin kasuwanci a Arewa, amma sai al'amarin ya koma har da iko ko mallakar qasa. An ce gwamnatin Ingila ta baiwa wannan kamfani maqudan kuxi wajen karvar iko da mallakar qasa, amma babu inda aka danqa masu wannan qasa. Haka kuma wannan kamfani na kasuwanci ba wanda ya sayar masa da qasar Arewa, a wurare da dama inda kamfani ya nuna iko a kan qasa sai al'ummar wajen su qaryata wannan magana.[4]

Ana cikin wannan gardamar ce sai Turawan Mulki suka zo, suka karvi qasar ta tsinin mashi. gwamnatin Mulki sai ta baiwa Cif Kwamishina ikon zartar da dokar mallakar qasa. Don haka aka zartar da hukuncin cewa duk wata qasar shugaban da aka ci da yaqi ko aka tuve, ta zama mallakar gwamnatin Ingila. Don

---

1 A.K. Medugbon, *Kaduna Nigeria*, shafi na 39

2 F.D Lugard, *Revision of Instructions to Political Officers*, Memoranda no. x London: 1919. shafi na 348

3 C.R Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na . 89-90

4 A.K Medugbon, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 39

haka da za su kafa garin Kaduna ba su nemi izini gun kowa ba babu kuma wanda ya ja da su da yin haka.

Tuddai da Qoramu

Garin Kaduna waje ne da ya kasance mai matsakaicin yanayi wanda bai cika zafi ko sanyi ba, a dai-dai tsakiyar Nijeriya ta Arewa. Waje ne mai tuddai da qoramu, yana kuma yanki da ake kira da Turanci "Savannah " wato daji wanda ba kurmi ba, amma akwai dogayen itatuwan doka tare da dogayen ciyayi waxanda ba su yi ruquqi irin na qungurmin daji ba. Wannan waje kuma yana da duwatsu jefi-jefi ba shi kuma da kwazazzabai masu yawa. Haka kuma akwai shi da issasshen ruwa daga kogi.

Shi wannan kogin Kaduna ya faro ne daga Gabas sannan ya gangaro ta tuddan Filato kusa da garin Jos, kana ya malala har zuwa Kawo kusa da Kaduna daga nan sai ya shigo garin ta kusurwar Arewa maso Gabas. Wannan kogi sai yanausa ya yi Kudu maso-Yamma har zuwa Kabala daga nan kuma sai ya miqe, ya doshi Arewa maso-Yamma, daga nan sai ya karkata Kudu, ya bi ta qarqashin gadar jirgi.

Kogin kan kawo har ma ya yi ambaliya a tsakiyar damina, amma wannan ambaliyar ba ta jawo wata asara domin babu gari ko qauye a wannan waje.[1] Babban hannun wannan kogi shi ne rafin Rigasa wanda qananan magudanan ruwa da lambatu ke janye ruwa daga unguwannin Yammacin kogin Kaduna.

Qasa da Tsire-Tsire

Ko da yake qasar Kaduna ba qasar noma ba ce kamar ta Arewacin Nijeriya, amma akwai qasar da ke da albarkar noma musamman a tsallaken kogi ta Yammaci da kudancin wannan waje, inda Gbagyi ke da mazauni. Qabilar gbagyi da ke zaune a waxannan wurare manoma ne. Akwai kuma wuraren noma a sassan wannan waje, saboda haka ne kamar yadda ake faxin qasar *Savannah*, qasa ce mai albarkar noma, Kaduna na cikin wannan yanki. Qasar Kaduna na da laushi da nauyi sosai amma duk da haka akwai tsire-tsire a wannan waje saboda dacewar yanayi.

Tsire-tsiren wannan wuri, irin wanda aka fi samu a yawancin sassan Arewa ne. Itatuwan wajen su kan yi girmasu kai qafa arba'in zuwa sittin, suna kuma da ganyaye masu faxi musamman a wajen gavar kogi. Waxannan itatuwa da ake kira doka suna da yawa sosai. A wannan waje a wasu sassa har akwai surquqi da ke da wuyar shiga. Saboda albarkar itatuwan doka a wannan waje ya sa ake kiran wajen da dajin doka. A lokacin da aka kafa garin Kaduna sai da aka buqaci mazauna garin da su riqa sare waxannan itatuwa saboda gudun hayayyafar kuxan tsando

[1] A.K Medugbon, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 32

wanda ke haddasa ciwon barci. Da aka sassare waxannan itatuwa sai aka shuka mangwarori sun kuma qawata garin sosai.

Waxannan dalilai su ne abubuwan da aka duba wajen kafa garin Kaduna. Wajen ya dace da yanayi da isasshen ruwa. Saboda Kaduna na tsakiyar Arewa sai Gwamna Lugga ya hango dacewarta da zama mahaxar hanyar jirgi. Daga wannan gari za a iya shiga jirgi zuwa sassa daban-daban. A taqaice dai wannan waje ya dace sosai da duk shika-shikan dalilai da gwamnan ke buqata wajen kafa hedkwatarsa. A lokacin da ake fafitikar tabbatar da Mulkin Mallaka, an fi so ne a kafa sojoji masu tsaro da shirin ko ta kwana a tsakiyar Arewa. Kaduna ta dace da yin haka. Daga wannan gari za a iya aikawa da askarawa a kusan duk sassan Arewa, idan buqatar yin haka ta taso cikin gaugawa. Hasali ma dai,, ba a shigo garin Hausawa ba ballantana a samu 'yar tangarxa da gidan Sarauta da Turawan mulki. Saboda waxannan dalilai sai Kaduna ta gamsar da 'yan kwamitin *Palmer* ta kowace fuska.

A wajen mallakar qasa kuwa Turawan mulki sun ba da hujjojinsu da cewa wannan waje mallakarsu ne. Saboda haka sai aka kafa gari a lardin Zazzau ba tare da an sami wata matsala da Sarkin Zazzau ba. Da farko garin Kaduna sai ya taso da baqin jini sosai. Saboda haka aka riqa yi wa garin da laqabi da: Kwari cikin daji, *A hole in the bush*; da Sakarcin Lugga, *Lugard's Folly*, da Faqon Goldsmith, *Goldsmith's Deserted Village*.[1]

Tsarin Gina Kaduna

Da farko sai da aka yi wa dajin doka qulaficin bincike don a tabbatar ya dace da a kafa gari. An kira masana masu kula da lafiya da tsabta don su yi wannan nazari. An kuma duba dacewar wannan waje ta fuskar isasshen ruwan sha da dacewar kasuwanci, da hanyoyi da sadarwa ta hanyar jirgi.[2]

A wajen tsari da safiyon gina garin kuwa an yi amfani da masana fanoni masu yawa. Wanda ya shugabanci safiyon wannan a waje, a shekarar 1913 shi ne Keftin Howel wani Jami'i xan leqen asiri da ke Rajimancin Arewa. Mista Collard shi ne Babban mai Safiyo daga Ikko, da Mista Fred Dawson muqaddashin Daraktan Fidaburdi daga Ikko; da Likita F. Manning, Babban Likita mai kula da lafiya daga Dungurun; da Likita C. Blair Babban Jami'in Tsabta; da Mista E. Cummins, masanin zana gini, wanda ya fara aikinsa a watan Maris na shekarar 1913, ya kuma kammala zana taswirar garin a watan Yuli na wannan shekara.

---

1 A.K Medugbon, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 45

2 NAK, Zarprof 1913. *Town Planning and Station Layout*

Waxannan masana sun kammala bincikensu sun kuma aikawa Gwamna rahotonsu.[1]

Waxannan masana ne suka yiwa garin kyakkyawan tsari wanda ya qunshi vangarori guda biyu. Vangaren Turawa daga kudancin gari da vangaren 'yan Qasa daga Yammacin gari an kuma yi duk yadda zai dace da tsarin Turawan mulki. A wata wasiqa da aka aikawa Gwamna, Mr. Dawson Muqaddashin Daraktan Fidaburdi, ya amince da tsarin amma ya ce an yi kuskure da ba a ba Turawa filotai masu girma ba.[2]

Garin Kaduna ya yi sa'ar samun kyakkyawan tsari da ya dace da zamani sannan kuma ya yi sa'ar samun shugabannin farko masu nagarta da adalci tare da aiki tuquru domin ci gaban garin. An kuma taso daga Dungurun zuwa sabuwar hedkwata a cikin tsari. Don haka aka tare a cikinsa ba tare da vata lokaci ba.

Tasowa Daga Dungurun

A shekara 1913 ne sai Gwamna Lugga ya dawo Arewa daga qasar *Hong Kong*. Dawowarsa ke da wuya sai Lugga ya cewannan gari ya cika zafi a yi maza-maza a tashi zuwa Kaduna. Kafin ka ce me har an fara qaura daga garin a cikin shekarar 1914. A wannan lokaci kuwa, Dungurun na da jama'a da suka yi yawan kimanin dubu talatin da biyar (35,000), amma ba da dukkansu aka taso ba. Waxanda aka taho da su Kaduna ba su da yawa sosai, ana yi masu laqabi da Dungurawa wato waxanda su ka yi zaman Dungurun.

A lokacin da tasowa zuwa garin Kaduna ya zama zahiri, sai aka yi wa ma'aikata bayanan tsare-tsaren tashin jama'a rukuni-rukuni, don a yi qaura a cikin tsari mai kyau. An kuma shaida wa jama'a rana da lokacin da kowane rukuni zai taso. An kuma tanadi taragun jiragen qasa da za su kwaso kowane mutum da iyalansa da kayayyakinsa ba tare da ya biya qudin jirgi ba, jama'a sun kagauta da su tashi su bar garin Dungurun.

Saboda matsaloli da ke gallabar mazauna Dungurun, don haka sai a kullum rashin dacewarta ke fitowa. Bayan da Gwamna Lugga ya sami qarin girma ya zama Gwamna Janar, sai ya ta da qaimi sosai na ganin cewa an bar garin Dungurun zuwa Kaduna.

Tun da yake an kammala dukkan muhimman ayyukan da aka shirya, akwai isassun gidaje da ma'aikatu da ofisoshi, sai aka shiga shirye-shiryen tasowa daga Dungurun zuwa Kaduna. Daga Dungurun an kwaso duk wani kayan gwamnati mai amfani, kamar gidajen katako, da injina iri-iri, da dai sauransu. Babban abin

---

1 *Ibid*, 15/1 A CC. 191

2 A.K Medugbon, *Kaduna, Nigeria*,15/191-3516/836/13: *Proposed New Capital at Kaduna*.

da ya kawo jinn tasowar daga Dungurun shi ne, varkewar yaqin duniya na xaya a shekara 1914. Amma a cikin shekarar 1917 kusan duk an tare a Kaduna.

A cikin qaramin lokaci, wato wajen misalin shekaru huxu (1912-1916), an shiga manya-manyan gine-gine a Kaduna. An yi waxannan gine-ginen cikin rahusa, saboda arhar aikin lebura da Turawan suka samu. An kashe fam dubu xari da goma sha-shida da xari xaya da hamsin (£116,150:00) wajen gina garin Kaduna kafin a tare baki xaya.

gwamnatin Mulkin Mallaka, ta taso zuwa Kaduna a ranar 16 ga watan Nuwamba na shekarar 1916. Ma'aikatar Fidaburdi a ranar 26 ga watan Nuwamba suka taso.[1] Amma Ma'aikatar Safiyo da Baitulmali da Sakatariya sai a qarshen shekara suka iso. Waxanda suka taso daga bisani su ne Ma'aikatar Lafiya da ta 'yan Sanda.

Ran 5 ga Janairun shekarar 1917 aka kammala tasowa daga garin Dungurun zuwa Kaduna. An fara turo sojoji zuwa wannan sabon wuri a shekarar 1913 inda aka girke su a garin Barnawa. Bayan sojoji sai aka turo Firsinino xari biyu da arba'in (240) da ma'akatan Kurkuku wato "Warders" guda saba'in (70) a qarqashin Mr. Caill wanda yake shi ne Shugaban Kurkuku. Nan da nan sai sojoji da ke Barnawa suka raka su zuwa gidan waqafi domin su qara ba da tsaro. A Dungurun ana yi wa Gidan Yari laqabi da "Gidan Kwalba. "[2]

Daga Firsinoni, sai Daraktan Fidaburdi wato *Public Works Department* da wani mataimakin Injiniya suka iso garin Kaduna, amma sai suka bar wani ma'aikaci Bature a Dungurun don ya tsaya ya kula da rusa gidajen da aka baro don a kwaso kayayyaki masu amfani, zuwa sabuwar hedkwata. Ma'aikatar 'yan Safiyo cikin tsakar daren tara zuwa goma na watan Disamba suka taso cikin gaggawa. Akwai 'yan Safiyo uku a cikinsu.

Bayan an kwana uku sai Mr. G. R. Matthews, Sakataren Lardunan Arewa ya iso Kaduna don ya rabawa ma'aikata ofisoshi da gidaje. Sakatariyar Mulki wadda ta qunshi vangaren filaye da ma'adinai, tana kuma da manyan ofisoshi guda goma da na Leftanar Gwamna da Sakataren Larduna. Waxansunsu sun iso kafin Kirsimeti, wasunsu kuwa sai bayan Kirsimeti suka zo Kaduna. Rukunin farko na ma'akatar Sakatariya sun riqa isowa da failolin ofis har ya zuwa shekarar 1915. Rukuni na biyu sun tsaya a Dungurun ne don su ci gaba da aikin mulki sai da aka kammala tasowa zuwa Kaduna suka taho daga baya.

Ana gab da hada-hadar bikin Kirsimeti sai Baitu-Mali ta taso zuwa Kaduna. A cikin ma'aikatanta akwai manyan ofisoshi guda biyu, an kuma iso da zunzurutun kuxi har fam dubu goma sha-xaya. A kuma wannan rana ce banki mai suna *The Bank of British West Africa* (BBWA) wanda ake kira, *The Standard Bank of West*

---

1 New Nigerian, Thursday, 5th January, 1967, shafi na 7

2 *Ibid.*

Africa a yanzu qarqashin Manajan Banki mai suna Mr. Amoore, suka taso zuwa sabuwar hedkwata.[1]

Ran 23 ga watan Disamba Ma'akatan Lafiya suka baro Dungurun zuwa Kaduna. Akwai Likitoci guda biyu da Nas Mata ko *Nursing Sisters* masu kula da majinyata guda biyu. Wannan rukuni yana qarqashin Likita Gordon-Hall, wanda shi ne Babban Likita wato *Principal Medical Officer*. Ran 28 ga watan Disamba, wato kwanaki biyar da tasowar ma'aikatan lafiya sai Auditor wato jami'i mai sa ido a harkar kuxi ya taso. Su kuma ma'aikatan Sadarwa ta P and T, wato *Post and Telegraphs Department*, sai suka biyo su a ranar 30 ga wannan wata.[2]

Leftanan Gwamna, Mista H.W. Goldsmith wanda yake shi ne madugu uban tafiya bai baro tsohuwar hedkwata ba, sai ran 4 ga watan Janairu na shekarar 1917. Wannan mashahurin Bature gwanin mulki bai iso ba, sai da ya tabbata Firsinoninsa sun sami mahalli. Ma'aikata kuma za a biya su haqqinsu, za a kuma kula da lafiyarsu. Ganin kowa na cikin walwala da farin cikin zuwa sabuwar hedkwatar, sai Mai girma Gwamba Goldsmith ya iso Kaduna inda ya buxe ofis xinsa a ranar 5 ga watan Janairu ba tare da vata lokaci ba. A wannan rana ce kuma qaramin mataimakin Sakatare ya iso da sauran ma'aikata tare da sauran takardun mulki. A kuma wannan rana 5 ga watan Janairun shekarar 1917 ce aka kafa garin Kaduna, a bisa doka da izini, don a wannan rana ce Gwamna ya tare a sabuwar hedkwata.[3]

Wannan sabuwar hedkwata an kafata bisa tsari mai kyau an kuma raba ta kashi biyu: Unguwar Turawa ko *European Settlement* da Garin Doka ko *Native Settlement*, " kamar yadda aka yi bayani. An yi haka ne saboda kowa ya zauna a mahallin da ya dace da addininsa, da al'adunsa ba tare da tsangwama ko qwamamawa ba. Amma saboda duk jama'ar da aka taso da su daga Dungurun zuwa Kaduna ba su da yawa, sai garin ya zama kamar faqo. Alal misali, a Unguwar Turawa, ma'akatan gwamnati farar hula haxe da 'yan Sanda da ma'aikatan Yari da Gidan Waya (P and T) dukkan jimillar waxannan mutanen ba su wuce ashirin da tara ba. Akwai bankuna guda biyu, da 'yan tsirarun ma'aikatan Relwe, da ofisoshin sojoji. Wannan rashin yawan jama'a shi ya sa sai ka ga gari kamar faqo don babu jama'a da yawa. Wannan ya sa a kai wa garin laqabi da Faqon Qauyen Goldsmith ko *Goldsmith's Deserted Village*.[4] Saboda a unguwar Turawa xaixaikun jama'a ake gani da gine-gine kyawawa, masu yawa.

---

1 New Nigerian, Thursday, 5th January, 1967, shafi na 7

2 *Ibid.*

3 *Ibid*

4 *Ibid.*

A garin Doka kuwa, layunka ba su wuce guda biyar ba da gidaje da ba su da yawa, waxanda suke xauke da jama'a da aka taso da su daga tsohuwar hedkwata. Mazauna wannan waje sun qunshi 'yan Nijeriya daga sassa daban-daban, da 'yan qasashen Afrika musamman daga qasar Saliyo da Ghana, waxanda da yawa daga cikinsu qananan ma'aikata ne.

To, idan aka ce garin Kaduna ana nufin Unguwannin nan guda biyu. Amma saboda saurin bunqasar garin ne sai nan da nan ya haxe da qauyukan da suke kewaye da shi kamar Barnawa, da Maqera, da Kakuri, da Kawo, da Kinkinau. A shekarar 1922 aka kafa Tudun-Wada. Bayan shekaru hamsin da kafa Kaduna yawan jama'ar da ke ciki bai wuce dubu xari da hamsin (150,000) ba, a watan Janairu na shekarar 1967.[1] Amma a watan Janairu na shekarar 2007 garin ya cika shekaru casa'in jama'ar cikinsa kuwa sun kai kusan miliyoyin uku. Har yanzu garin Kaduna bunqasa yake yana kuma xaya daga cikin manyan garuruwa ba a Nijeriya ba a Afrika baki xaya. Sai gashi Faqon Qauyen *Goldsmith* ya zama katafaren gari a cikin hanzari.

Su kuwa Askarawan Lugga da suka taso an sauke su ne a Maqera, a wajen Masaqar Kaduna wato *Kaduna Textiles Limited*. Waxannan sojoji sun qunshi: Sojan hedkwata wato "*Headquarters* " da na Farkon Bataliya da ake kira *First Battalion* " da rundunar 'A' kamfani da Rundunar 'E' kamfani da kuma "*Battery*. "

Sojojin kamfani su ne suka gina 'yan xakunan da za su tare cikin gaggawa, waxanda suke rufin ciyawa. Amma ofisoshi da yawa sun sami gidajen manyan ma'aikatan relwai, a ciki suka tare. Su kuma manyan Turawa hafsoshin soja, sai da ma'aikata Fidaburdi ta aiko da leburori don a gina masu gidajen da suka dace da su. Haka kuma a wannan waje ne aka gina wasu manyan gidaje da shaguna da xakin ajiye makamai.[2] Sojojin Nijeriya musamman 'yan Arewa sun yi sun wajen nuna bajinta da qwarewa a wajen yaqi. A dalilin haka ne aka sa masu suna Hausawan Ikko.

Waxannan Askarawa da suka fito da sunan Nijeriya a idon duniya, sun qunshi Hausawa da Nufawa da Kanuri da Azbinawa da sauransu. Kowa ce qabila na da yawa kamar haka:

Sunan Qabila	**Yawansu**
Hausa	1,171
Fulani	339
Kanuri	397
Arna	432

---

1 New Nigerian, Thursday, 5th January, 1967, shafi na 5

2 NAK, SNP 4087/1918. See also *Zarprof 2560 – Annual Report* No. 60, 1913 by Resident Freemantale J.M.

Zabarmawa	172
Dakarkari	147
Nufawa	63
Yarbawa	61
Shuwa-Arab	34
Yan Sanagal	16
Arewawa	8
Azbinawa	4
Jimilla	2,917[1]

Ita wannan rundunar Sojan WAFF ta na da askarawa da 'yan dakon soja Baqaqen Fata da suke da yawan dubu uku (3,000). Mafi yawa daga cikinsu kamar yadda qididdiga ta nuna a sama, Hausawa ne haka kuma mafi yawan rundunar 'yan Arewa ne. Wannan ya sa tun fil-azal ake wa sojan WAFF laqabi da "Hausawan Ikko. " *Sir Niven* Ya ce; "Cikin shekarar 1897 aka kafa sojan Afirka ta Yamma daga 'yan Sandan Kamfani. Da Turanci ana kiran su *West African Frontier Force*, a taqaice ana ce da su sojojin WAFF. Su sojan nan su a ke kira "Hausawan ikko. " Kuma sun shahara a Afirka ta Yamma saboda jaruntakarsu. "[2]

A tsakanin shekarar 1913 zuwa tarewar Gwamna H. W. Goldsmith a shekarar 1917, akwai manyan ayari guda biyu da suka tare a lokuta baban-daban. Tarewar Sojojin Tsaro kuma "Zakarun gwajin dafi " sun taso daga Dungurun zuwa Zariya a qarshen watan Disamba na shekarar 1912. A cikin watan Maris na shekara 1913 suka taso daga Zariya suka tare a garin Barnawa.

A watan Oktoba na wannan shekara kuma wasu rukunin leburori qarqashin Sarkin Alaro Malam Isa suka taso daga Dungurun zuwa sabuwar hedkwata domin a hanzarta gininta. Haka kuma an qara samun kwararowar leburori zuwa Kaduna daga Kano da sauran qasashen Arewa saboda neman aiki da kuma samun kuxin leburanci mai tsoka, wanda yake a wannan gari ne ake samun sisi a wuni wato sulai uku a mako. Wannan babban albashi ne a wancan zamani.

Wannan albashi mai tsoka ya janyo mutane daga sassan Arewacin Nijeriya. A cikin shekarar 1914 akwai leburori waxanda yawansu ya kai dubu guda da Magina xari da hamsin, amma kafin qarshen wannan shekarar har yawansu ya kai dubu xaya da xari shida da tamanin (1,680). An kuma samu qarin leburori da magina waxanda suka qaru zuwa xari uku da goma (310). Daga wannan lokacine aikin gini ya fara qara samun daraja, maginan da suka yi suna a wannan sana'a, sun haxa da Kura Birkila, da Malam Ibrahim Xanka, da Ndako Birkila. An daxe

---

[1] NAK, SNP 4087/1918. See also *Zarprof 2560 – Annual Report* No. 60, 1913 by Resident Freemantale J.M.

[2] C.R Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na 90.

aikin birkilanci da leburanci na jawo jama'a har na tsawon lokaci. Don kuwa har a shekarar 1926 kuxin leburanci a wuni sisi ne, babu kuma inda wannan garavasa take sai a Kaduna. Amma birkila kuwa yana samun sulai shida a mako wato sulai xaya a kowace ranar aiki. To, kada ayi tuya amanta da albasa. Ana ta bayanin gine-gine amma ba a ce komai akan ginin gidan Gwamna ba.

Gidan Gwamna Lugga

Gwaman Lugga ya zauna a Kaduna inda kuma ya yi mulkin Nijeriya a matsayin Gwamna Janar, daga shekarar 1913 zuwa 1918, amma gidan daya zauna bai daxe ba aka rushe shi. Da, wannan gidan yana nan qafa xari biyar daga Gidan Shawara wanda aka gina a shekarar 1948. Wato yana tsakanin gidan Mista *C.R Niven* da *Lugard Hall*, Yamma kaxan da layin *Coronation Crescent*. A wannan waje ne aka so a gina makeken gidan Gwamna wato *Government House Crescent*' amma wannan shirin bai yiwuwa.

Da Lugga ya bar Nijeriya bayan ya bar aiki sai ya bar wannan gida, sai Leftanan Gwamna *H.R Palmer* ya taso daga tsohon gidan Leftanan Gwamna *H.W Goldsmith* da ke gida mai lamba 20 a layin *Wharf* don ya tare a tsohon gidan Gwamna Lugga. An qayatar da wannan waje sosai. An yi masa randabawul mai ruwa wato *water tower*, a wajen titin shiga ta Arewa. An kuma shata titin fita ta Kudu mai faxi kuma mai tsawo sosai. Wannan layin aka sawa suna *King George's Way* don tunawa da *George* Sarkin Ingila na shida, wanda ya zama *Independence Way* daga baya. Wannan layi ya bi ta lambun gwamnati sai da ya dire da gavar kogin Kaduna a wancan lokaci.

A lokacin da Gwamna Lugga yake mulkinsa, ya kan bi wannan babban titi zuwa lambun gwamnati don ya shaqata a bakin kogi. Ya kan bi takan kadarkon da ake kira *Lugard's Foot Bridge* ko *Lugard's Suspension Bridge*, da ke kan wani rafi kusa da kogin Kaduna da ke wannan waje. Ta nan ya kan bi ya hau kwalekwale zuwa Barikin Soja da ke Barnawa. Layin *King George* yana tsakiyar layuka guda biyu: Layin *Prince Edward* (Ahmadu Bello Way) da ya shata tsakiyar sabon garin Doka da *Queen Victoria Way* (Tafawa Valewa Way) wanda yake qarshen unguwar Turawa ta fuskar Gabas.

A kan titin da ke Arewacin Gidan Shawara aka yi wani shatale-tale da aka qawata shi, da famfuna masu watsa ruwa. Sir Ahmadu Bello ya yi bikin buxe wannan shatale-talen da wata qungiyar masu kasuwancin ma'adinai suka ginawa Arewa. A wajen shagalin buxe wannan shatale-tale ne Sardauna ya yi bayani inda ya ce:

"Mai martaba Manjo Farrington, da masu girma Ministoci da Mata da Maza.

Ina so in nuna godiyarmu musamman ga wannan abu wanda zai taimaka wajen qawata babban birnin lardinmu, a madadin mutanen lardin Arewa, a

lokacin da nake karvar kyautar wannan sha-tale-talen ruwa wanda 'yan Qungiyar masu kasuwancin ma'adanai suka bayar. Wasu mutane sun xauka tilas ne haqar ma'adinai ta bar wasu tabbai ko ana so, ko ba a so, a bayan garinmu. Aikin da hukumar kula da ramun ma'adinai ta yi, ya yi maganin wannan, kuma abin farin ciki ne da Qungiyar masu kasuwancin ma'adinai ta tallafa wa qawata garin Kaduna a matsayin gudunmawarsu wajen bikin samun mulkin Arewa.

"Kai shugaba, ka tavo adadin ramun ma'adinai a jawabinka. Zan so in xan yi yabo a taqaice ga mazajen da suka kafa su. Rawar da mahaqa suka taka wajen gina lardinmu, musamman ma dai lardin Filato ba ta lissafuwa. Sun daxe tare da mu, kuma muna ji dasu, domin kuwa sun zauna tare da mu a lokacin da ake shan maxaci. Kamar yadda muka shiga namu "faxi tashi ", su ma haka. Kamar yadda muka shiga haka walwala da na tsukewa, su ma haka.

"Sunaye irin na su Foley da Lawes da Cooke da kuma Butter za su daxe a zukatanmu, kuma sun cancanci a tuna da su a matsayin na farko, waxanda da qwazonsu ne wannan Lardi ya kai matsayin da yake a yau. Zan yi butulci idan har ban qara da ambaton wani suna ba. Wanda mai yiwuwa ya riga mu gidan gaskiya, wannan kuwa shi ne Manjo Eric Wilson. A 'yan kwanakin nan shi ne kamar maganaxisu tsakanin gwamnatin lardin Arewa da masana'antar, da kuma xaukacin jama'armu. Ubangiji ya ji qansa amin. "Na ji daxi musamman da aka ambaci irin rawar da mutanen Afirikanmu suka taka a wajen haqar ma'adinai. Mun yaba da irin horon da aka ba 'yan Nijeriya, musamman 'yan Arewa, kuma mun yaba ganin cewa da dama daga cikin 'yan kasuwarmu sun fara shiga harkar lodi ta lodin kuza daga Filato zuwa Lokaja ne daga inda ake xaukarta ta ruwa.

"Rawar da masu hakar ma'adinai suka taka ba ta tsaya a kan kasuwanci ne ba. Sashen kufai na gwamnatin Tarayya ya amfana sosai da irin taimakon da mahaqan farko suka bayar wajen gano wasu wuraren tarihi da nuna su. Na tabbata cewa wannan sashe zai zama na farko na faxin irin tallafin da waxannan mutane suka yi masu, waxanda suka gano wasu kufen wasu al'ummomi da aka yi a Filato da sauran yankunan lardin a wajen haqe-haqensu. Sashen haqar ma'adinai aiki ne wanda ya rataya kacokan a wuyan gwamnatin Tarayya. Ba aiki ne wanda gwamnatin Lardi za ta iya yin doka a kai ba amma ma'aikatan kuza na Filato su kwana da sanin cewa, za mu kula da buqatu da jin daxi da ci gabansu, kuma mun yi imani da cewa mutanenmu za su sami qwarewa ta musamman da ilimin yin aikin.

"Ban tava xari-xarin faxar cewa gwamnatin tana maraba da zuba jari da ilimin qwararru daga qasashen waje ba. Na ga jawabin da aka yi a madadin aminina Ministan Lagos da Ma'adinai da kuma Qarafa a wajen buxe makarantar Aikin Ma'adinai a Jos a ranar 19 ga Disamba. Na amince jumlatan da da tabbacin da ya ba ku, cewa mu gwamnati Tarayya da lardin Arewa, a shirye muke mu cika alqawarinmu da muka yi wa waxanda suka zuba jari, kuma mu tabbatar da cewa

an karve su hannu bi-biyu su da dukiyarsu, kuma za a ba su duk goyon bayan da ya dace domin su bunqasa, ba tare da wani tarnaqi daga wasu Dokoki ba.

"Haka kuma dole ne in ce na yi farin ciki da na karvi wannan kyakkyawan sha-tale-talen-ruwa da xan lambunsa a madadin mutanen wannan lardi, wanda na amince zai taimaka gaya ba ma wajen qawata Kaduna ba, a'a, zai ma taimaka wajen lafiyar, masu abin hawa, masu wucewa a kan hanyar.

"Saboda haka, ina mai buxe wannan sha-tale-tale da sunan Allah, ina kuma fata zai zama mai amfani garemu da kuma al'ummomi masu zuwa. "

Ita kyautar wannan shatale-tale da Qungiyar Masu kasuwancin kayan ma'adinai suka baiwa Arewa a lokacin shagalin samun Mulkin Kai a shekarar 1959 ta taimaka wajen qawata wannan waje wanda shi ne cibiyar mulkin Arewa.

Kafa Sabon Gari

Dungurawa, maza da mata sun fara isowa wannan sabon wuri a cikin shekarar 1912, inda aka sauke su a wani waje, Yamma da tashar Jirgi ta Arewa wato tashar Doka. A wannan waje ne aka yi masu 'yan qananan gidaje kafin a gama tsara garin baki xayansa. A cikin jama'ar da suka taho daga Dungurun, akwai 'yan kasuwa da 'yan Janhol da ma'aikata iri-iri. Babban attajiri a cikinsu a wannan lokaci, akwai wani BaKano mai suna Maiburuji. Shi Maiburuji shi ne wanda ya zo da akwatuna ashirin da huxu cike da farin sulalla. A cikin 'yan Janhol kuma babu kamar Babbar Riga.

Dungurawa sun iso, sun tarar da babu kowa sai manya-manyan itatuwan Doka. Don haka ne aka yi wa wannan gari da suka kafa masa suna garin Doka. Wannan wuri, wato Doka, daga shi babu wani gari sai namun daji.

Saboda wannan sabon gari na maqwabtaka da garin Rigacikun daga Arewa da kogin Kaduna daga Kudu da Gabas, sa'an nan garuruwan Kangiwa da Kurmin Mashi daga Yamma sai waxannan garuruwa suka Kewaye shi. Amma leburori da yawa suna can bakin kogin Kaduna inda suka duqufa wajen aiki. Qarin leburori ya daxa bunqasa wajen. Zabarmawa da dama sun taho domin neman sana'ar leburanci.

A cikin jama'ar da suka taho daga Dungurun kuwa, akwai waxansu Baqaqen Fata mutanen Saliyo da Turawa suka taho da su. Su waxannan 'yan Saliyo sun taimaka qwarai wajen kafa wannan gari. Misali, Mista Thompson, wanda yake qwararren lauya ne, sai kuma Mista Acquah Ben, wanda yake shi ne akawun safiyo da sauran akawuna kamar su Mista Johnson da Mista Nortey, da Pa Victor Williams.

Bayan da Babban Baturen safiyo, Mista Collard ya yi safiyon garin baki xaya, kuma ya kammala aikinsa, sai aka zo ba da filayen gina gidaje a inda ya kamata da a kafa Garin Doka. Shi wannan Sabon Garin Doka, shi ne wajen muhallin

jama'ar gari don su zauna wajen da ya dace da addini da al'adunsu. A inda aka gina wa Turawa gidajensu, nan ne ake kira Unguwar Turawa. Su mutanen Sabon Garin Doka da kansu suka gina gidajensu yadda ya dace da rayuwarsu. Kowa ya gina filotinsa dai-dai qarfinsa.

Lokacin da aka zo ba da filayen yin gidaje, sai aka buqaci kowane mutum ya biya sulai biyar kafin a shata masa fili mai tsuwon yadi xari da faxin yadi hamsin. Mista Acquah Ben shi aka danqa wa wannan aiki, wato aikin safiyon gari.

Mutumin farko da aka fara bai wa fili, shi ne shahararren xan Janhol xin nan mai suna Babbar Riga, shi aka fara shata wa filin gida a layin Kwantagora. Daga nan sai akawun Safiyo ya shata wa magatakardan Gwamna, Liman Malam Jafaru filin gina gida a Layin Shaba. Sarkin Alaro Malam Isa shi ne na uku an bashi fili akan layin *Prince Edward*.[1] Daga bisani sai aka bi sauran jama'a aka ba su filayen gina gidaje. A hankali sai rukunin jama'a suke tahowa daga inda aka ba su masauki, a kudancin tashar jirgi ta Arewa suna tarewa a gidajinsu. Tun da wannan sabon garin Doka, garin Dungurawa ne ba a bai wa kowa fili ba sai da aka kammala ba su tukuna. Mista Acquah ya qwarewajen aikin safiyo, duk shi ne ya yi safiyon garin baki xaya.

Domin a yi garin cikin tsari, kamar yadda Mista Collard ya ba da umarni, sai aka shaci wani layi babba wanda ya fi faxi da tsawo, shi wannan layi sai aka sa masa suna layin *Prince Edward*. Duk sauran layuka kuma su kan faro ne ko kuma su qare da wannan layin. A hankali sai Dungurawa da tsofaffin sojoji suke zuwa, sai layukan suka ci gaba da qaruwa.

Qarewa yaqin duniya na farko a shekarar 1918, yasa tsofaffin sojoji sun daxa bunqasa garin Doka, don haka sai layuka suka ci gaba da qaruwa kamar titin Haxeja da na Katsina. Dungurawa da tsofaffin sojojin da suka yi yaqin duniya na farko, su ne suka nome itatuwan doka da ke waxannan wurare suka kuma tayar da gidajensu a layuka daban-daban.

Inda aka gina gidan Gwamna Lugga kuwa, shi ne wajen da aka gina Gidan Shawara a yanzu wato *Lugard Hall*. An gina barikin soja wato Magadishu Barracks; bayan da aka gama ginin wannan bariki ne, sai sojoji suka taso daga barikinsu da ke Kakuri suka dawo cikin garin Kaduna.

Babban titin *Prince Edward* ya tsaga Sabon-Gari, ya faro tun daga tashar Doka har ya zuwa bakin gadar jirgi, sai ya raba garin Kaduna biyu. Fuskar Gabas, shiyyar ma'aikata da fuskar Yamma kuma ta 'yan kasuwa ne. Wannan babban layi an sanya masa suna layin *Prince Edward* ne saboda tunawa da ziyarar da xan Sarkin Ingila Yarima Edward wanda ya kawo ziyara Arewa har aka yi masa hawan bangirma a birnin Kano a cikin shekarar 1925. Wannan layi shi ne titin Ahmadu Bello a yanzu.

---

[1] Hira da Malam Tnimu Zariya ran 15 ga Agusta 1984

An ci gaba da tsattsaga layuka a unguwar Turawa. An tsaga wani babban layi a wannan unguwa wanda ya taso tun daga gidan Gwamna Lugga, sai da ya haxe da lambunsa da ke bakin kogin Kaduna, wato lambun gwamnati a yanzu. Wannan layi shi ne *King Georges Way*. A wannan lambu Gwamna ke shaqatawa, idan ya fito daga gidansa, sai ya taho miqe har zuwa lambun sa, bayan gwamnan ya gama shaqatawa, sai ya shiga cikin jirgin ruwansa ya bi kogin Kaduna zuwa Barnawa wajen sojojinsa. A cikin shekarar 1954 aka xauko wata gada wadda gwamnan ya yi amfani da ita a garin Dungurun. Ita wannan gadar wato *Lugard's Foot Bridge*, an kawo ta wannan lambu don qayatar da shi da kuma tunawa da Gwamna Lugga. Wannan waje ake kira Qofar Gamji a yanzu.

Unguwanni da Layukan Dungurawa

Dungurawa da suka fara isowa Kaduna a shekarar 1913, an sauke su a Kudu da Fidaburdi wato wajen Asibitin 44 inda suka gina gidajen zana da bukkoki. A hankali sai unguwa ta tashi a wannan waje saboda samun sauqin haya da mahalli. Akwai wata mata buzuwa mai sana'ar abinci sai aka riqa yiwa wannan unguwa laqabi da "Unguwar Buzuwa. " A shekarar 1914 sai hukuma ta hana gina gidajen zana barkatai da gina gidaje ba da izini ba.

Ita wannan unguwa sai ta ci gaba da havaka ta nemi ta zama matartarar zauna gari banza. Da ganin haka sai aka tashi wannan unguwa, mutanen unguwar kuma suka koma Abakpa. A wajen da aka tashi Unguwar Buzuwa ne aka kafa Asibitin 44. Da yawa daga cikin mazauna wannan unguwa sai suka koma Tudun-Wada.[1]

Kamar yadda aka yi bayani an kasa garin Kaduna kashi biyu. Yankin Unguwar Turawa wanda ake kira *European Reservation Area* da yankin 'yan qasa da ake kira *The African Reservation Area* ko *Native Settlement*. Vangaren mazaunin 'yan qasa ma ya rabu kashi biyu. Yankin Doka da Yankin Sabon Gari.

A yankin doka aka sauke ma'aikata, a wajen da ake kira Doka. Mai yiwuwa ya samo wannan suna ne daga itatuwan doka da suke birjik a wannan waje. Wannan yanki, ya rabu kashi biyu saboda bambancin gine-gine da zaman jama'a. Wannan vangaren doka kuwa yana kusa da ma'aikatar Fidaburdi da ke Arewa da Sabongari. A wannan vangare ne Dungurawa suka fara tarewa a yankin 'yan qasa na wannan sabuwar hedkwata. A wancan lokaci kuwa wajen da gidan Gwamna yake a yanzu kuma Kudu da Tudun-Nufawa na cikin vangaren doka.

Wannan vangare yana da gidaje masu rufin kwano, don haka wannan yankin ake wa laqabi da *Zinc Way*. A wannan zamani gidaje masu rufin kwano a Arewa basu da yawa, babu inda ake samunsu a duk faxin Arewa sai a wannan unguwa. A xaya yankin wannan unguwar kuwa an gina gidajen da qonannun tubali. Da waxannan tubala aka gina wani vangaren wannan unguwa don haka a ke wa

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu ran 15 ga Satumba 1984

wannan unguwa laqabi da *Brick Way*.[1] Irin wannan samfurin gine-gine ma sabo ne a Arewa.

A yankin gidaje masu rufin kwano aka sauke ma'aikata. Yanki mai ginin qonannun tubali kuwa aka sauke akawuna ana kiran wajen yankin akawuna ko *Clerk Quarters*. Ita wannan unguwar ma'aikata ce. Akwai kasuwa a cikin kowane yanki na wannan unguwar Doka. A wannan unguwa ne aka fara saukar da wasu Dungurawan Lugga kafin yawancinsu su gama gina gidajensu a sabon gari. Amma saboda bunqasar wannan unguwa cikin hanzari, sai wasu ma'aikata suka koma sabon gari saboda unguwar ta cika.

A yankin Sabon Gari jama'a ne suka gina gidajensu da kansu. Ga Layukan Da Dungurawan Lugga suka kafa gidajensu:

Layin Kwantagora

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Babbar Riga, da Sarkin Fawa Muhamman, da Kwasau, da Qoqori Xan Malam, da Sharu Tunku, da Sarkin Fawa Xangero, da Gambo Mahauci, da Audu Keffi Aboki Fari, da Audu Keffi Aboki Baqi, da Jambuku, da Gambo na Xangero, da Sarkin Fawa Adamu, da Galadiman Kwantagora, da Dala da Audu Fari da Namarashe, da Nakarara, da Hamidun Nakarara, da Sharu Na Anaca da, Sarkin Maqera, da Tabalo Mai Tuwo, da Rakiya Gwamna, da Magaji.

Layin Shaba

Ana kiran wannan layi da sunan wani Banufe mai suna Shaba, wanda yake zaune a layin. Qarshen layin kuma ana kiransa Gangaren Jos. Shaba fitaccen xan kasuwa ne wanda ya yi suna sosai har aka sa wa unguwar da yake zaune da "Unguwar Shaba. " Ita wannan unguwa ta qunshi layukan Bida, da Argungu, da Jos, da Kano, da kabba, da layin Nupe. Akasarin mazauna wannan unguwa Nufawa ne. Nufawa sun ba da muhimmiyar gudunmawa wajen bunqasar sabon garin Doka suna kuma da babban tasiri a ci gaban Kaduna. Saboda tasirantuwarsu ne har Gwamna Goldsmith wanda ya jagoranci tarewa a Kaduna ake masa laqabi da Gwamna "Akube laji. "[2] Waxanda suka kafa wannan layi su ne: -

Liman Malam Jafaru, da Umaru Liftagu, da Adamu Tsohon Soja, da Nda Gimba da Adamu, da Farida Nafargore, da Dijen Badarawa, da Sarkin Magina Bahaxeje, da Mai Katako da Garma Xan Audu, da Malam Sir'idu Banufe, da Malam Inuwa Uban Jibrin Xan Gambari, da Cakwa, da Rejimanci Malam Baqo, da Shatu Mai Qarfin Doki, da Malam Inuwa Mai Kura, da Fatin Kuku, da Xan

---

1 New Nigerian, Thursday, 5th January, 1967 shafi na 7

2 *Ibid*.

Wanzam Banufe, da Malam Ahmadu, da Maiyaqi Zuru,da Nakanda, da Gaidan Maikaji, da Malam Mamman Na Wala, da 'Yar Sanda.

Ita 'Yar Sanda wata Bakanuwa cewadda ta yi tashe a garin Kaduna. Sana'arta sayar da tuwo ce ta bunqasa arziqinta. Saboda Kaduna garin leburori ne, sai kowane lebura ya tabbatar yana da kwano a wajenta wanda za a saka masa tuwon, ba leburori kawai ba, har ma mahauta ma, su ma kuxin tuwon su suke ba ta, saboda ba kasafai suke komawa gida ba idan sun tafi kwata ba. Don haka sai su bar mata kuxin abincinsu.

Ta haka ne ma kusan kowane magidanci sai ya bar kuxin abinci ga iyalansa a kowace rana, wannan shi ne dalilin bai wa iyalai kuxin abinci a garin Kaduna. Ban da 'Yar Sanda, Tabalo Mai Tuwo ita ma ta yi nata tashe a wajen sayar da abinci.

'Yar Sanda ta shahara wajen sana'ar abinci, don bunqasar wannan Bakanuwa, sai ana wa Kaduna kirari da ita. A kan ce "Kaduna ta 'yar Sanda lahirar makwaxaita. " Da farko dai jama'a da yawa suna zuwa Kaduna don su shiga aikin soja ko na xan sanda. Akasarin su sun gudo wa hukuma ne daga garuruwansu, don haka idan suka gudo zuwa Kaduna, suka kuma shiga aikin Sarki, to, sun tsira ke nan. A wannan zamani an xauki aikin Sarki kwaxayin abin duniya ne, shi ya sa ake wa Kaduna kirari da lahirar Makwaxaita. Duk wanda ya zo da wuya ya koma garinsu saboda samun sakewa da jin daxin zama.

A kan ce da Kaduna "Kaduna ta 'yar Sanda mai kadarko da tsawo, ke wargi ba a kawo maki wargi, kina mai kamar kya ba yaro riga amma ta wuyansa kike nema " Wannan na nuna bunqasar mutanen Kaduna da kuma rashin jure wulaqancinsu, gari ne kuma wanda idan mutum ya zo da nufin komawa gida sai ka ga ya yi zamansa.

Layin Prince Edward

Waxanda suka kafa wannan layi su ne: - Sarkin Alaro Malam Isa, da Audu Na Malam, da Jatau Yola, da Kwakwalagi, da Mista Amawo, da Mista Nortey, da Malam Nuhu Sarkin Maqera, da Mai Damisa, da Baqo Mai Mota, da Baban Bawa, da Malam Aminu Ilori, da Malam Ta'idu (mai gobe da nisa), da Sarkin Haquri, da Mista Sagoe Mai Burodi, da Daddy Foto, da Abubakar Bamaiyi, da Malam Sharif, da Barankaca, da Gambo Direba, da Adamu Wushishi, da Madam Kashi Kano, da Habiba Zariya.

Layin Kano

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Sarkin Hausawa Babale, da Sadau Soja, da Mai Buruji, da Musa nki, da Malam Rafa, da Audu Na Sarkin Kano, da Garba Tasawa, da Korau Dillali, da Mista Johnson, da Samanja Gaji, da Usman Uban Ndababo, da Hauwa Tarwaxa Baki Kamuwa Koda Haki, da Bagobiri Xan

Janhol, da Samanja Gindin Kura, da Musa Tanko, da Tankon Na Mai Buruji, da Sadau Mijin Aya, da Liman Malam Musa, da Malam Baffa Gwambe.

Layin Haxeja

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Bukar Mandara, da Dariya, da Garba Tela, da Shehu Mai Siyasa, da Mista Ladipo, da Ungulu Xan Sarkin Lakwaja, da Madaki Wushishi.

Layin Jos

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Binta Mai Alayyaho, da Andi Mai Awo, da lya Mamman, da Malam Mai Xan Baki, da Malam Jibrin Mai Qarfe, da Malam Usman, da Umaru Xankoli,da Mai Salati, da Malam Audu Boyin Bature, da Ahmadu Tafintan Kantoma, da Mista Thompson, da Malam Xanjatau, da Auta Mai Awo da Muhammadu Masinja, da Malam Isa Tireda, da 'Yar Mai Koko, da Xan Wanzan, da lya Jirgin Bauci Mai Wuyar Kwana, da Dauda Mai Kanwa, da Ta'adayi, da Malam T.A. Morrow, da Bakale, da Gaidan Mai Kaji, da Madugu Birkila.

Layin Gwandu

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Sarkin Alaro Bagobiri Baban Baito, da Belu Makerin Sarki, da Musa Xan Audu Wanzami, da Xan Sakkwato Mai Turare, da Usman Maqeri, da Sarkin Mutane Malam Hussaini.

Layin Katsina

Shi wannan layi wani Bakatsine ne, kuma tsohon soja ne, mai suna Gwanda Majemi ne ya fara zama a wurin. Saboda bayan da aka gama Yaqin Duniya na xaya ne sai shi Gwanda ya koma aikinsa na Jima, don haka ne aka fito da shi wajen gari a inda yaci gaba da aikin jima. Sauran waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Nanan Jiniya, da Abara Mai Tuwo, da Goma Makaho, da Malam Muhammadu Zangina, da Malam Mamman Mai Kanwa Basakkwace, da Malam Bashari, da Alabi, da Xan Magaji Sanqira.

Layin Ibadan

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Adamu Mijin-Shatu Mai Qarfin Doki, da Xan duniya Direban Gwamna, da Titi Mai Kuxin Kotu, da Malam Musa Bussa, da Inuwa Magini, da Xan Gambari, da Sarkin Yarbawa Oga Dada, da Shatu Gindingyare, da Malam Ali Mai Yanka, da Madam Kwantagora.

Layin Kabba

Waxanda suka kafa wannan layi su ne:- Muhammadu Xan Qosassa, da Ibrahim Xankaza, da Buraimoh Tafinta, da Yakubu Tela, da Malam Garba Mai Kaji.

Sauran Dungurawan da suka kafa layuka a wurare da dama su ne:- Mamman Zinda Odilan Gwamna, da Sarkin Zango Malam Dodo, da Liman Malam Jiya, da Buda, da Gambo Jaki, da Nakauru, da Babaraba, da Natatuko, da Abdul-Salamu Bakanike, da Mista Okonkwo, da Usman Dogo Mai Kwaxo, da Linzami, da Sambo Algazaru Maganin Kuxin Zamani, da Maimuna Kwantagora, da Ali Maihaquri Sarkin Dillalai, da Majidaxin Dillalai, da Mista Onyeagoro Mai Jankunne, da Mista Bassey, da Mista Silver, da Mista Ramson, da Mista Viictor Williams, da Mista Solo, da Mista Watson, da Mista *Acquah Ben*, da Mista D. I. Emudo, da Mista Naty.

Dukkan waxannan layuka da aka lisafta, za a samu mutum guda ya zauna a layuka fiye da biyu saboda wadatar fili da sauqin samunsa, don haka zai yi wuya a tabbatar da tahaqiqanin waxanda suka fara kafa layi tun da ba abu ne a rubuce aka tarar ba. An yi wannan abu ne don a xan nuna wa jama'a yadda layuka suka fara kafuwa, akwai Dungurawa da tsofaffin soja masu yawa wanda wannan littafi bai kawo su ba.

A duk inda jama'a suka taru suka kafa gari, suna gina wajen ibadarsu. A zaman Sabon Garin Doka akwai Musulmi da Kirista zaune a wannan gari, saboda haka ne aka samu masallaci da Maja'mila.

Masallacin Farko

Masallacin Juma'a na farko a garin Kaduna shi ne na Titin Kano. An gina masallacin ta hanyar taimakon jama'ar garin, kuma manyan attajirai da shugabannin wannan lokaci sun taimaka sosai wajen gina masallacin. Attajiran da suka bada gudunmawa mai tsoka su ne; Sarkin Fawa Muhamman da Mai Buruji, sannan da shahararren shugaba Malam Aminu Ilori. Da taimakon waxannan bayin Allah da sauran jama'ar gari da kuma taimakon Sarkin Magina Adamu Bahaxeje aka gina wannan masallaci.

Limamin farko shi ne liman Malam Jafaru daga nan sai Liman Malam Musa. Sauran limaman su ne, Liman Malam Jiya da Liman Malam Sule Xan Liman Ja'afaru da Liman Malam Adamu sannan sai Liman Abdullahi da Liman Xan Zariya.

Gina Sabon Masallaci

Garin Kaduna ya shiga qarni na ashirin da xaya, *21st Century*, da rikice-rikicen addini da qabilanci. A shekarar 2000 ne aka yi wani mummunan faxan addini tsakanin Musulmi da Kirista. A wannan lokaci ne aka qona

masallatai da majami'u da dama a wannan gari. A cikin masallatan da aka qona har da tsohon masallacin garin Kaduna na Kano road. Wannan abu ya tayarwa mazauna wannan gari hankali matuqar gaske. Saboda haka sai aka nemi taimakon jama'a don a saka ginin wannan masallaci. A cikin wannan shiri ne sai aka kafa 'Yan Kwamiti na musamman don a cimma wannan manufa.

Alhaji (Dr) Umar Dikko, tsohon Minista a gwamnatin Shehu Shagari aka naxa ya shugabanci wannan Kwamiti na sake gina masallacin. Alhaji Lawal Husaini wani sanannan malami shi ne Sakatare da Alhaji Ibrahim Bata a matsayin mataimakin Sakatare. 'Yan wannan kwamiti sun nuna himma, gaskiya da riqon amana wajen wannan aiki wanda jama'ar garin Kaduna ke zakwaxin an gama shi da gaggawa saboda babu wajen sallar *Hamsus Salawati* da sallar Juma'a.

'Yan Kwamitin sun fuskanci matsaloli da yawa wajen aiwatar da wannan muhimmin aiki. A wannan lokaci suna buqatar isassun kuxi don su sake gina wannan tsohon masallaci su kuma faxaxa shi. Bugu da qari tilas ne a hanzarta gina tsohon masallacin da aka qona domin jama'a su riqa samun wajen *Hamsus Salawati* da sallar juma'a kamar yadda aka saba. Wannan shi ne qalubalen da suka fuskanta na farko.

Suna cikin halin yaya za mu yi ke nan sai Allah Ya turo wani bawan Allah attajiri mai suna Alhaji (Dr) Aliyu Abubakar Shugaban Kamfanin A. A. Oil, ya je wajen Dr. Umar Dikko yana buqatar a bashi wannan aiki na sake gina wannan qonannan tsohon masallaci. Ya kuma shaida wa shugaban wannan kwamiti cewa, "Zan gina shi yadda ku ke so, in Allah Ya yarda. "[1] Saboda haka sai shugaban ya kira taro na gaggawa don a tattauna wannan batu da wannan attajiri ya gabatar. A zaman da suka yi sai suka zartar da a bashi tsohon masallaci ya sake gina shi.

Kafin ka ce me! Har Dr. Aliyu Abubakar ya laqwame wannan aiki, ya gina masallaci mai hawa biyu irin na zamani ya kuma qawatar da shi da kayayyaki masu kyau wanda ya dace da zamani. Domin har xakin Taro wato *Islamic Conference Hall* aka gina, a hawan farko na wannan masallaci.

A ranar 19 ga Oktoban shekarar 2003 aka yi bukin buxe wannan masallaci. Mai girma Atiku Abubakar, GCON, Turakin Adamawa, Mataimakin Shugaban Qasar Nijeriya ne ya buxe wannan masallaci a gaban xaruruwan mutane, manyan malamai da Sarakuna da shugabanni. Jama'ar Kaduna kuwa ba wanda ya fi su farin ciki a wannan rana. To, amma kuma wannan masallaci ya yi qanqanta sosai saboda garin Kaduna a kullun bunqasa yake da jama'a kuma harkokin Addinin musulunci qaruwa su ke yi a koda yaushe. Saboda haka sai ya zama tilas a gina xaya vangaren wannan masallaci a kuma faxaxa shi. Wannan shi ne qalubale na biyu da 'yan kwamiti suka fuskanta.

---

[1] Hira da Alhaji Lawal Husaini, Sakataren Kwamitin Gina Masallaci, ran 6 ga Disamba 2009.

Idan ana buqatar a faxaxa wannan masallaci, to, ya zama tilas a saye gidajen da suke kusa da shi, musamman gidan Mr. Green, wani Ibo xan Kaduna kuma sanannan xan Siyasa a garin Kaduna. Ko da yake ya daxe da rausuwa sai 'yan kwamiti suka nemi xansa wato magajinsa *Mr. Chris Mbadiwe* da ya sayar masu da wannan gida wanda shi da masallaci an qana su saboda ana buqatar a faxaxa masallaci. To da *Mr. Chris* yaji wannan buqatar 'yan kamiti sai ya ce da su:

"Yanzu lokaci yayi." Ya kuma fassara wannan kalami da xan taqaitaccen tarihi, a inda ya ce, "A shekaru da dama da suka wuce, Firimiya Sir Ahmadu Bello, ya buqaci mahaifina Mr. Green da ya sayar masa da wannan gida domin yana so ya faxaxa wannan masallaci. A wannan lokaci kowa har mahaifina na ganin girma da mutuncin Sardauna saboda haka babu abin da zai tambayi mahaifina ya hana shi. Amma buqatar da yasar masa wannan gida ta tayar wa mahaifina rai sosai. Domin baya son ya sayar da wannan gidan ba ya son kuma ya vata wa Sardauna rai.

"Saboda haka sai ya aika da wata tawaga ta musamman zuwa ga Firimiya domin su rarrashe shi su kuma bayyana masa dalilan da ba zai sayar masa da wannan gida ba. Domin wannan gidansa ne na tarihi wanda shi ne No. 1 Prince Edward wato Ahmadu Bello Way. Har-ila-yau wannan gida shi ne Hedkwatar NCNC a Arewa a zamanin Siyarsa Farko. Saboda haka Sardauna ya yi haquri da waxannan dalilai domin suna da muhimmancin gaske a gare shi da zuriyarsa.

"Firimiya ya ji daxin wannan bayani sosai ya kuma ce ya gode, a kuma shaidawa Mr. Green cewar ai musulunci bai yarda a qwaci fili ko gidan mutum don a gina masallaci ba. Saboda haka bai yi fushi da rashin sayar da gidansa ba. A dalilin wannan tarihi ne nace daku, yanzu lokaci ya yi. "[1]

Mr. Chris Mbadiwe ya ce muna alfahiri da wannan gida a wannan garin amma tun da lokaci ya yi sai mu sayarwa masallaci das hi. Ya qara da cewa, ai babu wani mahaluki da zai sa mu sayar da wannan gida komin kuxinsa domin wannan gida ya gagari kundila. Amma za mu sayar da shi don alfarmar masallaci. Ya kuma yi rangwame sosai wajen sayar da shi. Duk da haka 'yan kwamiti ba su da kuxin sayen wannan gida sai sun nemo taimako.

Qalubale na uku da 'yan kwamiti suka fuskanta shi ne samo kuxin sayen gidan Mr. Green na Binta. A wannan lokaci sai suka yi shawara da a tuntuvi Mai girma Atiku Abubakar, Turakin Adamawa. Shi ma ba tare da vata lokaci ba sai ya bada gudunmawar kuxi mai tsoka wajen sayen wannan gida. Nan dan nan aka sayi wannan gida aka kuma rushe shi don a gina masallaci babba.

---

[1] Hira da Alhaji Lawal Husaini, Sakataren Kwamitin Gina Masallaci, ran 6 ga Disamba 2009.

Idan aka dogara da taimakon taro da sisi waxanda za a samu daga jama'a, to, ginin wannan masallaci zai xauki shekaru. A kuma halin rashin kuxi da jama'a ke ciki baza a dogara ga wannan hanya ba. To, daga qarshe sai 'yan Kwamiti suka yi shawar das u rubutawa gwamnan Jihar Kaduna Mai girma Dr. Ahmed Mohammed Maqarfi buqatar da ya taimaka wajen gina wannan masallaci.

Shi ma Gwamna bai vata lokaci ba, sai nan da nan a kafa na sa kwamiti da za su yi aiki kafaxa da kafaxa da kwamitin masallaci. A cikin xan qaramin lokaci sai Mai girma Ahmed Mohammed Maqarfi da Abokansa suka haxa hannu suka gina wa garin Kaduna wani katafaren masallaci irin na zamani. Wanda hasumayarsa tayi sama ta haskaka samaniya. Babu shakka wannan masallaci ya dace da garin Kaduna hedkwatar Arewa.

An yi shagalin bikin buxe wannan sabon masallaci ranar juma'a 19 ga watan Muharram 1427 AH wanda ya yi dai-dai da 17 ga Fabrairun shekarar 2006. Imam Shaykh Hassan Ali Cisse kuma Babban Limanin masallacin Madina Baye da ke Kaulaha ta qasar Senegal ne ya buxe wannan masallaci a gaban ximbin jama'a manyan mutane, Sarakuna da shagabanni. A wannan rana ce hankalin jama'ar garin Kaduna ya sake kwantawa suka shiga hamdala da farin ciki don Kaduna ta samu masallacin day a dace da it.

Malam Aminu Ilori da taimakon attajiran gari ne suke fara gina wannan masallaci akan Kano Road bayan Dungurawa sun tare a Sabon Garin Doka. Bayan kusan shekara ar'bain da biyar sai Firimiya Sir Ahmadu Bello ya bai wa Alhaji Audu Bida Kwangilar gina wannan masallaci wanda zai dace da zamani. Daga nan sai a shekarar 2003 Dr. Aliyu Abubakar ya sake gina wannan masallaci don ya dace qarin bunqasar jama'a da zamani. Amma aikin faxaxa masallaci da sake masa fasali sai Alhaji Ahmed Mohamemd Maqarfi da Abokansa suka xauki nauyin wannan aiki wanda aka gama shi a 2006.

Wannan masallaci ne da ya taso cikin sa'a da albarka a kuma cikinta yake Abadan. Saboda haka Allah Ya sakara dukkan bayin Allah da suka taimaka wajen sake gina wannan msallaci da Alhairai masu waya, amin. Har ila yau watahila aikin wannan masallaci ya farfaxo da aikin taimakon miskinai da naqasassu a garin Kaduna.

Taimakon Naqasassu

A farfajiyar masallacin garin Kaduna ta yankin Kano Road da Hadeja Road miskinai da naqasassu suka mayar ya zama mahallinsu. An samu shekaru masu yawa waxan nan bayin Allah na zaune a wannan waje. A lokacin Gwamna Alhaji Abdulqadir Balarabe Musa ne gwamnatinsa ta gina Gidan Miskinai da Naqassasu amma sai zama da kula da su, suka gagara saboda haka da yawa daga cikinsu sai suka maida masallacin garin Kaduna da ke Kano Road Mahallinsu. To, gashi an sakewa wannan masallaci fasali an kuma faxaxa shi da qawatarda shi sosai saboda

haka sai zamansu a wannan waje bai dace ba. Amma yadda za a tashe su sai ya zama matsala. Domin bai kamata a yi masu xiban Karan mahaukaciya ba.

Alhaji Dr. Aliyu Abubakar ne ya bada shawarwari cewa ai bai kamata a fara maganar tashin waxannan miskinai ba sai in an samar masu waje da ya dace da su koma. Saboda haka sai umurci 'yan kwamitin masallaci dasu nemo wajen da zai saya don ya gina masu mahalli. Nan da nan sai aka samu wasu filaye a wata fadama da ke qarshen Katsina Road, a cikin waxannan filaye har dana Alhaji Zakariya'u Dankulla guda biyu wanda ya bayar kyauta don taimakon miskinai sauran kuma Dr. A. Abubakar ya sayesu kuxi hannu wuri na gugan wuri.

Kafin ka ce me! Har wannan attajiri ya gama gina wajen mahallin miskinai da naqasassu irin na zamani. Saboda haka sai ya buqaci waxannan bayin Allah da ke layin Kano Road da Haxeja Road da ke zaune a harabar masallaci das u taso su tare a wannan waje. Shi ne ma kan gaba wajen yiwa waxannan bayin Allah jawabi wanda ya kwantar masu da hankali. A cikin ladabi da tausayi Dr. Abubakar ya ce da ximbin naqasassu da miskinan masallaci:

"Assalam alaikum, babu shakka ku 'yan uwanmu ne waxanda Allah Ya nufa da zama wannan wuri. Amma wannan wuri bai dace da ku ba saboda lokacin damina ku sha dukan ruwa da bazara kuma lokacin hunturu sanyi da iska su addabe ku. Saboda haka sai muka tanada maku wani waje mafi dacewa inda zaku sami wajen kwana da hutawa. Kun ga yanzu an gyara wannan masallaci an kuma qawatar da shi saboda haka zamanku anan bai dace ba. A dalilin haka ne ake buqatar da ku tashi ku koma wancan matsuguninku na zamani. "[1]

Miskinai da naqasassun wannan masallaci sun ji daxin bayanin wannan attajiri sun kuma tafi wajen da ya gina masu, suna godiya ga Allah da ya azurta su da wannan bawan Allah, mai tausayi da jinqai. Ya kuma ba su taimakon kuxi don su tashi ba tare da samun wata matsala ba. Irin wannan aiki na taimakon ta miskinai da gajiyayyu yana da muhimmanci sosai.

A zamanin Sarakuna a Siyasa, aikin kula da naqasassu a na bashi muhimmanci. A lokacin da aka kafa Makarantar Makafi ta koyon sana'a a Kaduna a shekarar 1954 babu irinta a duk faxin yankin Afirka ta Yamma. Jihar Arewa ce a gaba wajen taimako da nuna tausayi da jinqai ga miskinai da naqasassu. A wannan fanni Sarakuna da shugabannin Arewa sun nuna kyakkyawan misali.

A Zamanin Firimiyan Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello, Sardauna Sakkwato shi ne Shugaban Qungiyar Taimakon Makafi ta wannan Jiha. Sir Abubakar da

[1] Hira da Alhaji Lawal Husaini, Sakataren Kwamitin Gina Masallaci, ran 6 ga Disamba 2009.

Shehun Barno Sir Umar Muhammadu El-Amin El-Kanemi su ne manyan shugabanin wannan qungiya. Haka zalika lokacin da za a buxe Makarantar Makafi, gwamnan Arewa, Sarakuna da Shugabanni duk sai da suka hallara, aka yi qasaitaccen shagalin biki kamar na buxe jama'a, domin idan aka baiwa naqasassu irin wannan tallafi an ceto dubban 'ya'ya da jikokinsu daga cikin mummunan qangin da suka sami kansu saboda naqasar iyayensu ba tasu ba.

Gini da Tsarin Layi

Kowane Badungure, Mista Acquah ya ba shi fankacecen fuloti, don haka da yawa daga cikin masu wannan fulotai sai suka yi marhabin da mutanen da suka zo daga sassan Nijeriya don zamantakewar juna. Ana kiran su tsofaffin zuwa wannan Sabon Gari. Wasunsu sun ba da isasshen fili ga waxannan baqi da su gina xakunansu domin zaman tare, wasu kuma xakunan sun bayar da su haya ne, a hankali sai garin ya tashi havaka.

Zuwan jama'a daga sassan Nijeriya, ya bunqasa sana'ar gini, saboda haka maginan kusa da na nesa sai bankowa suke ta yi don samun sana'ar gini. Jama'ar da suka kafa Sabon Garin Doka, su ne suka gina gidajensu iya qarfinsu. Galibin gidajen jinka ne, ginin soro sai mai hali, wato attajiri. Sarkin Maginan Sabon Garin Doka shi ne Adamu Bahaxeje. Amma saboda jama'a da yawa na buqatar gini sai magina suka riqa zuwa daga qasashen Zariya, Kano da kuma Katsina. Waxanda su kan zo daga Zariya, akwai Sarkin Magina Maiingoto, Malam Manzo da Malam Kwasau, Malam Inuwa Magini daga Kano, Muhammadu Magini daga Katsina. Sauran maginan su ne Malam Garba Uban Sharubutu da Kurman Xan Gambari.

Waxannan magina sun taimaka qwarai wajen gina Sabon Garin Doka. Idan suka fara aiki daga asubahin fari zuwa Yamma suna da albashin sule da sisi (18d), kuxin lebura a wuni kuwa kwabo huxu (4d). Wannan albashi mai tsoka ya jawo jama'a da dama zuwa wannan gari domin neman aiki. Su maginan suna gina gidajen cikin tsari, kamar yadda aka yi safiyo tsakanin layuka biyu ana barin xan qaramin layi wato xan kwararo inda ruwan qazantar gidajen layukan zai bi ya gudanye ya wuce ta bayan gida.

Saboda yawan gobara da ake samu kuma dukiyoyin jama'a da dama na salwanta, sai Turawa suka ba da umarnin cewa kowane magidanci ya yi qofofi guda biyu a gidansa, wato qofar gida da qofar bayan gida domin shiga da fita ko *Entrance and Exit*. Da ya ta shiga gida, xayar kuma ta fita ta bayan layi, saboda ko da gobara ta varke, to, mutanen gidansa samu hanyoyin ceto rayukansu da dukiyoyinsu, 'yan Sanda da ke aikin kwana-kwana ko kashe gobara ba su da yawa a wannan lokaci, har ma ya zamana ba su iya aikata komai in gidajen layi guda suka kama da wuta, amma idan an yi qofa a bayan layi, to, jama'a sa samu sauqin asara.

Wani abin takaici da yin qofar bayan layi ta haifar shi ne sai varayi suka sami damar shiga gidaje ta bayan layi don yin sace-sace, da an biyo su sai su arce ta qofar bayan layi. Wannan ya sa jama'ar gari suka zama ba su da sakat, idan an toshe qofar bayan layi, farmakin gobara ya gallabe su, in kuma an bar wannan qofa sai a shiga artabu da varayi. Haka dai jama'ar wannan lokaci suka yi ta xauki-ba-daxi tsakanin gobara da varayi, har tsawon zamani mai nisa. Ganin irin wannan wahala da jama'ar garin ke fama da ita ne, sai Turawa suka sanya dokar hana yawon dare, ko jama'a sa samu sauqin 'yan sace-sace da ake yi masu.

Bayan da gari ya havaka, sai aka sa lambar gidaje domin cika adireshi saboda kowane layi yana da sunansa. Daga Layin Shaba aka faro ta gidan Nda Gimba da ke kan kwana. Wannan gida ya fara da A1, gidan Fargore A2, gidan Ali A3, gidan M. Sambo A4, gidan Audun Dede A5 da haka sai da lambar duk ta zagaye gidajen garin baki xaya. Sunan layuka da lambar gidaje sun kammala adireshi ke nan.

Majami'un Farko

An yi limaman majami'u masu yawa kuma mabiya xariku daban-daban, a wannan gari, sun kuma taimaka da ta su gudunmawar wajen bunqasa addinin Kirista a garin Kaduna. A cikin 'yan shekaru kaxan, an gina majami'u masu dama. Majami'ar farko ita ce ta C.M.S. da ke titin Ibrahim Taiwo wadda aka kafa a cikin shekarar 1919.

Sauran majami'un su ne Majami'ar 'Baptist' ta layin Haxeja da Majami'ar 'Catholic' ko 'Saint Joseph Cathedral Church' da ke titin Ibrahim Taiwo da 'Saint Christopher's Church. Shi wannan tsohon Coci ne wanda a nan ne Turawa suke ibadarsu. A wannan Majami'a ce aka xaura auren 'Yar *Sharwood Smith*. Majami'ar *Angilican*, sannan da Majami'ar U.N.A. (United Native Authority), da ke layin Katsina wadda aka gina a shekarar 1934.

Limaman waxannan majami'u suna da yawa, amma ba za a manta da kamar su Bishop Mort, da Bishop John, da Bishop Macarthy ba. Sauran su ne Reverend Ohara, da Reverend Stit, da Reverend Minihamme, da Reverend Faulkner, da Reverend Olafimihan da Bishop Segun har ya zuwa Reverend Peter Jatau. Waxannan limamai sun taimaka sosai wajen karantarwa da wayar da kan jama'a akan addinin Kirista.

Majami'ar farko da aka gina a Kaduna ita ce ta St. Christopher's Anglican Church da ke kan titin Sokoto daura titin Independence Way Dungurawa Kiristoci mabiya xariqar Anglican Faith a Kaduna, sun fara taron yin ibada a Kakuri, a gidan wani mutumin qasar Ghana mai suna Mista J. B. Sagoe, tun a shekarar 1915. Akasarin Dungurawa Kiristoci mabiya xariqar Ebenezer Anglican Church ne, saboda haka da zuwansu Kaduna sai suka haxa kansu, suka kafa wajen Ibada a Sabon Gari. Amma mabiya xarikarsu da ke Kakuri sai suka rabu kashi biyu.

Kashi guda na waxannan mabiya, sai suka haxu da na Ebenezer da ke Sabon Gari suka kafa wata Coci, da ake kira St. Michael Church, wadda ita ce Cocin Anglican ta farko a Sabon Gari. Amma kashi na biyu na Kiristocin da ke Kakuri, ba su taso zuwa Sabon gari ba, sai suka kafa wata babbar Coci mai suna St. Paul's Church a Kakuri. Majami'ar Anglican ta farko a Kaduna, an kafata ne a inda gidan Gwamna yake a yanzu. An yi gini ne na xan wani lokaci da aka yi da laka da rufin ciyawa, an yi masa dakalin laka a wajen zaman masu ibada.[1]

A shekarar 1917 aka gina Coci ta biyu a Sabon gari. Mista G.R. Matthews, wanda yake Sakataren Lardunan Arewa, shi ne ya aza harsashin gina wannan Coci, a ranar 24 ga watan Afrilun shekarar 1917 a wani waje da ke kusa da African Club. Wannan Coci na da faxin xaukar mutum xari.[2]

A watan Maris na shekarar 1920 wata qungiyar Kiristoci mai suna Nigeria Pastorage Association ta bai wa Cocin Anglican filin da aka gina St. Michael's Cathedral Church a yanzu.[3] An fara aikin gina Cocin a shekarar 1922. An yi aikin gayya wajen gina wannan Majami'a, a inda jama'a maza da mata da 'yan makaranta suka taimaka wajen kwaso yashi daga kogin Kaduna. Mazaje kuma suka taimaka wajen aikin birkila da kafinta da fenti da sauransu. Ana yin wannan aikin gayya ne da Yamma bayan an tashi aiki. Bishop A.W. Smith ne ya kaxxamar da wannan Majami'a, a ran 2 ga Oktoban shekarar 1927.[4]

Mabiya xarikar Cocin Katolika, sun gina Majami'arsu ta St. *Patrick's* Roman Catholic Church a shekarar 1916, a qarqashin jagorancin Revered Fr. Gately. An kafa wannan Coci akan titin Lagos da ke daura titin Haxeja. Daga nan sai aka samu qarin majami'u masu yawa kamar St. George's (CMS) Church, a qarqashin jagorancin Reverend Odusanjo a shekarar 1919, da *United African Church* (U.N.A) a qarqashin jagorancin *Reverend* Barber. Haka kuma a shekarar 1920 masu bin xarikar *Baptist Mission* suka fara taruwa wajen ibada a qarqashin Mista P.A. Okesanjo a garin Kaduna.[5]

Kowace xarika na da Cocinta, mabiyan waxannan xariku kuma na zaman lafiya da juna. Kiristoci a garin Kaduna suna nuna haxin kai sosai. Saboda kowa da kowa na aiki tuquru wajen kyautata ibadarsa da kyautata wajen ibadarsa da kuma raya jin daxin mabiya xariqarsa ba tare da wata tsangwama ba. Har-ila-yau ba a samun hargitsi ko tashin hankali a tsakanin waxannan dariku. Saboda sun yi imani abin da ya haxa su, ya da ya raba su qarfi.

---

1 E. O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na 330

2 *Ibid*

3 NAK, SNP 9 2698/1922

4 Crampton F.shafi na T., *Christanity in Northem Nigeria, Zaria*, Gaskiya Corshafi na , (1975), shafi na 141

5 E. O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na 331

Kamar yadda aka samu bambanci a wajen ibada, haka aka samu bambanci wajen karatun boko a wannan gari. Akwai Makarantun Mishan da Makarantun gwamnati.

Makarantun Mishan

Makarantun Mishan ne aka fara kafawa a garin Kaduna. Daga baya ne aka samu makarantun gwamnati. A watan Maris na shekarar 1919, aka gina makarantar St. Michael (CMS School). Ana jin wannan ita ce makarantar farko da aka fara gina wa, bayan da aka zartar da dokar kafa makarantun Mishan a shekarar 1918.[1] Ita wannan doka ta gindaya sharixun da za a cika kafin a kafa makaranta. Daga wannan makarantar sai aka gina, makarantar "RCM School " a shekarar 1920 da ta *Baptist Mission School* a shekarar 1921.

Waxannan makarantu sun bambanta akan xarikun addinin Kirista, da qabilun da suke fi bin wannan xarika. Alal misali, qabilar Ibo tafi yawa a makaranta RCM School; Yarbawa kuma sun fi yawa a Baptist School, amma ita CMS School sai ta zama ta haxa qabilu mabiya xariku da dama. A rahotonsa na qarshen shekarar 1929, muqaddashin Daraktan Ilimi na lardunan Arewa, ya ce akwai wata 'yar makaranta a unguwar Munci.[2]

Makarantun na koyar da rubutu da karatu ana kuma horar da 'yan makaranta hanyoyin watsa Bishara. Turawan Mulki sun sa ido qwarai da gaske wajen ganin abubuwan da ake yi da darussan da ake koyawa yara sun dace da qa'idojin da aka shimfixa wa waxannan makarantu. Duk da haka an xauki matakin ganin Kiristocin Arewa sun fi Musulmi ilimin boko, domin a cimma wannan muradi, sai aka daqile ci gaban makarantun gwamnati ta hanyar biyan kuxin makaranta mai yawa, tare da rage darussan da ake koyar da xalibai. Saboda waxannan dalilai ne ya sa har yanzu Kiristoci ke kan gaba a fagen ilimin boko a Arewa.

Ilimin Boko da Makarantun Gwamnati

Turawan Mulki, domin su cimma shirin su na wariyar addini da yanki, sai suka raba bayar da ilimin boko a kan bambancin addini da na qabila. Dalilin haka yasa aka qirqiro makarantu gwamnati domin kula da 'ya'yan ma'aikata da akawuna da ke zaune a Sabon gari. Dalilin wannan shirin ne aka kafa makarantun En'e a Zariya da Kaduna.[3]

An gina makarantar gwamnati ta farko, a kusa da kasuwa a watan Janairu na shekarar 1919. Ita wannan makaranta ta fara da yara sittin masu shekaru shida

---

1 NAK, SNP, 17/9944, *Mission Schools in Northern Nigeria*.

2 *Ibid*., CSO 26/2/11852 Vol. VII: *Education Dept., Annual Report* for 1929.

3 E.O. Oyewole; *Colonial Urbanization*, shafi na 336

zuwa bakwai. Amma tsarin koyarwa da manhajar makarantar kamar na 'yan Kudu suke. An fara da biyan kuxin makaranta kwabo goma (10d), amma sai aka riqa qarin kuxin har sai da ya kai sulai biyu da sisi. Wannan kuxin makaranta ya daqile damar da dubban yara za su samu na ilimin boko, saboda biyan wannan kuxi sai manyan ma'aikata da attajirai a wancan zamani. Ba a fara da ba yara kayanzuwa makaranta ba, wato *school uniform* amma makarantar na ba su littattafan rubutu. Makaranta na xaukar hutu a ranakun jumma'a da lahadi.

Da farko kuma ana koyar da su Turanci, da rubutu da karatu, da lissafi, da *Geography*, da *Elementary Hygiene*, da *Physical Education* da Gardening.[1] Amma abin takaici shi ne ba a koyar da Turanci da ilimin kimiyya a Makarantun gwamnati da 'ya'yan Musulmi ke zuwa ba sai a shekarar 1943. Kafin wannan lokaci kuwa an sami babban givi ko tazarar ilimi a tsakanin Musulmi da Kirista da ke zaune a Arewa. Wannan shiri ba a Kaduna aka aiwatarda shi ba har ma da duk sassan Arewa.

Daqile Musulmin Arewa ta fuskar ilimin boko, wani muhimmin shiri ne da Turawan Mulki suka aiwatar domin kafa wata kutingwilar hana ci gabansu, da zai yi tasiri a shekaru masu zuwa. Rashin koyar da Turanci a makarantun Elementare ta En'e da ke garuruwan Musulmi ya kawo cikas wajen koyar da ilimin kimiyya, wanda darussansa da turanci ake karanta su da rubutasu a littattafai masu yawa. Saboda haka babu yadda wanda bai san turanci ba zai samu ilimin kimiyya. Gwamna C.L Temple, wanda yake wani jigo ne wajen aiwatar da wannan shiri, ya yi qoqarin bayyana dalilan yin haka da kalami kamar haka: "A cikin shirin Mulki takan Sarakuna wato *Indirect Rule* bai haxa da koyar da rubutu da karatu da turanci ga yara ba, saboda yin haka zai sanya matasa tasowa da halayya da xabi'un Turawa. Domin duk wanda ya fito daga makaranta ya kan rabu da jama'arsa. "[2]

A lokacin da aka yi amfani da wannan bayani, la'akari aka yi da qyama da tsoron da 'yan Arewa ke nunawa karatun boko saboda ta wannan hanya ce, makarantun Mishan ke yaxa Bishara ga yaran Musulmi. Dalilin haka ya sa Turawa suka fake da haka, suka kafa kutingwilar daqile ci gaban Musulmi ta fuskar ilimin kimiyya da fasaha; suka kuma qirqiro wata babbar tazara tsakanin Musulmi da qananan qabilun Arewa, waxanda suka qarvi addinin Kirista sau da qafa. Abin da Turawa ke nufi shi ne, tunda ba ku qarvi addininmu ba, kuma kuna qyamar xabi'u da al'addunmu, saboda haka ba za mu ba ku ilimin zamani da muka zo da shi ba.

A makarantun gwamnati da aka kafa a Kaduna, akwai yaran Musulmi amma ba su da yawa saboda tsadar kuxin makaranta. Dalili yin haka kuwa shi ne domin ya zama martani daga Turawan Mulki ga Musulmin Arewa. Dalilin haka yasa tun

---

[1] NAK, SNP 17/2 10,207

[2] E.O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na 3

a tashin farko, ilimin boko a garuruwan Musulmi ba na talaka ba ne. Ilimi ne na 'yan tsiraru wato ilimi ne na 'ya'yan manyan ma'aikata da attajirai da Sarakuna. Har yanzu waxannan matsaloli da Turawa suka kafawa ilimin boko a Arewa, ba a samu shawo kansu ba suna kuma yin mummunan tasiri ga ci gaban al'ummar Musulmi.

Mista M.N. Oakes shi ne hedmasta na farko, a makarantar gwamnati da ke Kaduna, daga shi sai Mista A. Savage. Makarantar na da 'yan Kwamiti da suka qunshi Turawa da 'yan Afrika. Wannan kwamiti kuma na da mambobi guda shida waxanda suka haxa da: Sakataren lardunan Arewa, da *Station Magestrate*, da *Superintendent of Education*, da Mista Bruce Faulkner da ke Sakatariyar lardunan Arewa, da Mista P.D Quartey na *Audit Department*, da Mista J.A. De Veer na kamfanin *Niger Company* da ke Kaduna Jamsin.

A shekarar 1926 akwai mambobin kwamitin wannan makaranta da aka sansu sosai, waxanda suka haxa da Mista B.L.A Kenneth wanda a wannan lokaci shi ne *Station Magestrate*, da Mista R.F.S. Pary, *Superintendent of Education* da Mista A. Savage wanda ya zama hedmasta shi mutumin qasar Saliyo ne. Saboda ana samun yawan sauye-sauyen ma'aikata ya sa ake samun sauye-sauyen 'yan kwamitin makaranta.

A shekarar 1928 'yan kwamitin shugabancin wannan makaranta sun haxa da: Sakataren lardunan Arewa, da *Superintendent of Education*; mai kula da makarantu a Kaduna, da Mista T.B. Batten wanda a wannan lokaci shi ne *Station Magestrate* da Mista P.G. Da Silva, da Mista E. Alawode da Mista A.G. Reffel.[1] A wannan lokaci an ba da sunan Malam Aminu Ilori, wani qasaitaccen attajirin da ke Kaduna domin ya zama xaya daga cikin 'yan kwamitin wannan makaranta.

An gina wata makarantar Elementare a Maqera a qarshen shekarar 1928. Aka ce an kafa ta ne domin ta zama kariya daga illolin makarantun Mishan a wannan waje.[2] A shekarar 1929 akwai makarantu guda bakwai a Kaduna: "Makarantar St. Michael (CMS *School*), da ke kusa da Barikin 'yan Sanda, da R.C.M. *School* da ke kan *Broadcasting* Road, kusa da kasuwa, da *Baptist School* da ke kan Haxeja Road, da *United Native African School*, da ke kan Katsina Road, da makarantar *Methodist*, da makarantar gwamnati da makarantar Elementare ta En'e da ke Maqera.[3]

---

1 NAK, SNP, 17/2 10,207.

2 E. O. Oyewole, *Colonial Urbanization*, shafi na 3

3 *Ibid*. shafi na 340.

Tsofaffin Zama

Samun aikin yi da zaman lafiya da walwala sun taimaka gaya wajen kwararowar jama'a zuwa Kaduna. Rukunun farko na waxannan jama'a ne ake kira da tsofaffin zama. Su ne suka zo da safiyar fari bayan tarewar Dungurawa.

Ga kaxan daga cikin tsoffafin zama, su waxannan su ne suka zo dab da kafa garin, su ne kuma suka fara taya Dungurawa zaman gari. Zuwan waxannan jama'a ta havaka garin sosai, waxannan an bayar da sunayensu domin ba da misali kawai daga cikin jama'ar tsofaffin zama.

Layin Shaba: Inna Umma, da Kada, da Dalo Mai Fenti, da Malam Shehu Gidan Na Fargore, da Malam Bawa Magini, da Sani Mila, da Jatau Munci, da Malam Awaisu, da Malam Uban Doma, da Daniya, da Hussaini Mai Doya, da Mara, da Uwar Tagwaye, da Malam Usman, da Audun Dede, da Audu Xangungu, da Malam Zakari, da Habiba Alqalin Mata, da Shattun Burus, da Malam Sambo Kuku, da Zara Marwa, da Danga Mai Kaji, da Malam Umar Qiru Na Malam Baqo.

Layin Prince Edward: Malam Garba Na Mai Damusa, da Yusufu Tela, da Muhammadu Raji Maihaja, da Mista Green Na Binta, da Ibrahim Mai Kirci, da Laraban Kwakwalagi, da Mai Gemu.

Layin Kwantagora: Hauwa Gwari, da Alhaji Ilori Xan Koli, da Malam Ango Tela, da Sule Azare Direba, da Magaji Maigoro.

Layin Kano: Malam Kwalo, da Gade Kariya, da Xan Sakkwato Mai Jaki, da Sharu Bida, da Uwa Mai Shinkafa, da Samanja Gindin Kura, da Musa Tanko, da Hadiza Mai Tuwo, da Tafa.

Layin Haxeja: Kuri Mai Shinkafa, da Malam Muhammadu Kori.

Layin Lagos: Abdussalam Bayarabe, da Mamman Tela, da Xahiru Mai Azara, da Musa Kwabo, da Fulani Mai Goro, da Xan Zariya Mai Mangwaro.

Layin Jos: Haruna Mahauci, da Alhaji Nagaga Mai Goro, da Xan Zariya Maijinka, da Fati Mandara, da Sule Gaya Printa, da Ali Birkila, da Malam Audu Masinjan Kantoma, da Alhaji Banife, da Mai Gwari Ma'auni, da Shu'aibu Uban Saude Mahauci, da Bala Mai Turare, da Amadi Mai Wanki, da Xan Zariya Mai Kilishi, da Malam Xanjatau, da Audu Kafinta, da Malam Maude Dillali Zariya, da Baban Korau Mai Kilishi, da Hajiya Uwa, da Muham-madu Masinja, da Xan Mikici.

Layin Gwandu: Muhammadu Kachan Mai Awo, da Muhammadu Dunkurki Mai Awo, da Malam Ali Mai Awo, da Xan Magaji Mai Molo, da Hussaini Mai Goro, da Malam Abubakar Mai Saje, da Malam Mamman Mai Babban Gemu Maiduguri, da Xan Magaji, da Autadun.

Layin Katsina: Bashar Mai Qirgi, da Ibrahim Na Haro, da Isa Zuru, da Milio, da Jaji Rabi, da Umar Muni, da Fulani Mai Goro, da Ladan Majemi, da Ya'u

Majemi, da Malam Bashari, da Zubairu Mai Shinkafa, da Ahmadu ka fi Sarkin Qauye (Don ba shi da albashi), da Mijin Yawa Maroqi, da Zubairu Maijinka, da Xahiru Maijinka, da Xahiru Mai Azara, da Xankargo Mai Azara, da Ya'u Mai Azara, da Tinau Maqeri.

Layin Binuwai: Laraba Kwakwa, da Alhaji Banufe Mai Gyaran Agogo, da Kuku Xan Zabarma, da Malam Amadu Na Ta Jatau, da Malam Bala Tela, da Malam Mato Magini, da Ali Xan Ikko, da Sarkin Pawa Yusuf, da Mu'azu Maigini.

Layin Bida: Malam Madugu Birkila, da Talle Mai Tuwo Gangaren Jos, da Mai Tuwon Bola, da Samanja Alhaji Usman Kano, da Sambo Rano, da Malam Raji Birkila, da Maimuna Tanko, da Hajiya Mairiga, da Balogun Sarkin Yarbawa.

Layin Kabba: Mairam Matar Malam Baqo, da Mista Obe, da Sarkin Lakwaja, da Audu Uban Acici, da Garangaran, da Magajiyar Gari.

Layin Adamawa: Shattu Gwambe, da Hajiya Yalwa, da Rejimanci Mamman Pakai, da Malam Shayo Mai Unguwa, da Samanja Musa Banana, da Fatin Famfo, da Hauwa Mai Gashi.

Layin Kalaba: Uba Xan Ta'adayi, da Malam Ibrahim Sabuwa, da Mamman Xangidan Rubu, da Hussaini Mai Doya, da Haruna Na Haro.

Layin Benin: Ibrahim Firdabudi, da Xan Mami, da Malam Nuhu Sarkin Maqera, da Narogo, da Malam Banufe, da Fati Samanja Ringim, da Audu Xan Kano, da Ana-Rubu, da Beben Xan Gambari, da Malam Mai Saifi, da Yamutsi, da Abdulqadir, da Malam Amadu Dinko Mai Dala, da Mista Eze, da Mai Gwari, da Alhamdu Atiya (Fari), da Musan Babuwa, da Samanja Mamman Jimma, da Abdul-Aziz Mai Injin, da Xanjummai Maidoya, da Alhaji Ahmadu Bakutumbe, da Alhaji Lawal Xan Koli, da Alhaji Audu Gajere Mai Turare, da Malam Bala Keffi, da Sharu Usman Dillali, da Alhaji Banufe.

Layin Warri: Malam Muhammadu Aduba, da Tankon Tumburi, da Hauwa Sakkwato, da Mamman Tambaya, da Malam Bala Mai Awo, da Sabuwa Mai Awo, da Jibrin Tela, da Sarkin Bauci, da Bala Sarkin Kasuwa.

Layin Zariya: Sansam Zariya, da Ibrahim Maiqirgi, da Alhassan Direba, da Hassan Sajen Gobe, da Roqi Mai Kalangu, da Xahiru Mai Azara, da Abu Mai Goro, da Malam Sirajo, da Malam Audu Mai Saifi, da Gambo Mai Motar Asibiti, da Tagari Uwar Kaduna.

Layin Kaduna: Malam Baffa, da Malam Bala Dillali, da Mai Kano Direban Gwamna, da Alheri *Service*.

Layin Gold Coast: Yusuf Mijin Adugwa Mai Turare, da Xan Fulani Dillali, da Yaro Gire, da Kuku, da Alhassan Bayarabe, da Sarkin Maqera, da Audun Banki.

Layin Ibo: Malam Audu Mai Tatsuniya, da Malam Yahaya Qanin Malam Sirajo, da Malam Ibunu.

Layin Abuja: Malam Attahiru

Layin Ogbomosho: Badamosi Bayarabe, da Patrick Makanike.

Layin Ibadan: Sarkin Nufawa Maliki, da Misis Rossy, da Alhaji Maigishiri, da Audu Fala-Fala, da Jatau, da Baba Korau Mai Kilishi, da Ladin Tunisaye.

Layin Wushishi: Bazamfare Mai Tsire, da Shattun Kaila, da Laran Bayero

Layin Argungu: Haruna Xan Birni, da Xan Sakkwato Mai Awo, da Magajiya Mai Awo, da 'Yar Maqera.

Shugabannin Farko

Duk inda jama'a suka taru daga cikin abubuwan da za su buqata shi ne shugabanni, ba domin komai ba sai don tafiyar da sha'anin yau da gobe cikin lumana kuma bisa qa'ida. Shugabannin farko a cikin wannan Sabon Gari sun taimaka qwarai da gaske wajen bunqasar wannan gari, da kuma fito da Kaduna ta zama wata aba a Nijeriya. Shugabanni sun sadaukar da kawunansu, sun yi aiki tuquru domin bunqasar mazaunan garin a wannan lokaci.

Su waxannan shugabanni su ne jigon tafiyar da mulkin Gwamna Lugga da kuma sauran Turawan mulki baki xaya, don kuwa ba qaramar sa'a Turawa suka yi ba, da suka samu nagartattun shugabanni waxanda suka taimaka qwarai da gaske. Domin sun nuna qin kansu wajen gina al'ummarsu. Saboda sadaukar da kawunansu da waxannan bayin Allah suka yi, ne ya kamata mu ji kaxan daga taimakon da suka bayar don bunqasar garin Kaduna xin.

Malam Isa Sarkin Alaro (Labour Leader)

Malam Isa, mutumin garin Kura ta qasar Kano ne, ya tafi garin Dungurun daga makarantar Allo ta Yadakwari. A garin Dungurun ne yaci sarautar Alaro (Labour Leader), a shekarar 1905. Shi ne ya shugabanci leburorin da suka yi aikin shimfixa hanyar jirgin Baro zuwa Kano a cikin shekarar 1907-1911.

Malam Isa da rundunarsa ta leburori, tare da Turawan aiki suka fara tahowa dajin Doka domin gina Kaduna sabuwar hedkwata a cikin farkon shekarar 1912. Ban da waxannan ayyuka da suka yi, aikin shugabancin leburori abu ne mai wuya qwarai da gaske.

Ba kai hanyar jirgi zuwa biranen Zariya da Kano ke da wuya ba, a'a, zirga-zirga da wannan jirgi tsakanin waxannan garuruwa, shi ne mai matuqar wuya. Shi wannan jirgi na wannan zamani aiki yake da itatuwa ba kwal ba. Aikin Sarkin Alaro na farko, shi ne ya tabbatar da jirgi na zirga-zirga tsakanin Kaduna zuwa Zariya. Tun da wannan jirgi yana amfani da itace ne kafin a gano amfani da kwal, don haka dole ne a tabbatar da an samu itatuwa isassu saboda wannan jirgi. Leburori aikinsu ne su bazama cikin dawa, suna saro itatuwa, su sassabesu, su kuma datsa itatuwan gudil-gudil misalin tsawon qafa bibbiyu. Shi wannan itacen gudil-gudil, wato makamashin jirgi shi ake kira "Kwakwalagi. "

Idan babu Kwakwalagi, to, jirgi ba ya iya zuwa ko nan-da-can. Wannan shi ya sa kullum Malam Isa da leburorinsa suna cikin daji safe da Yamma, suna ta sarar itatuwan Kwakwalagi.

Idan an tara isassun Kwakwalagai, sai a kwaso su a zuba su tsibiri-tsibiri a gefen hanyar jirgi dama da hagu, tsakanin wannan tsibiri da wancan nisan ya kai yadi 150. In an kammala shirya su xin ne sai ka ga tsibiren Kwakwalagin sun tafi bila-adadin. Leburori sun riqa yin sintiri ke nan a kan hanyar jirgi har zuwa Zariya, suna kuma jera itatuwan kwakwalagi a hanya, idan sun gama aikin wannan ranar, sai su biyo jirgi su dawo, kashe-gari kuma su komasu ci gaba da duba hanya, duk inda aka kwashe itatuwan, sai sun kai madadinsu.

Duk inda jirgi ya yi sanyi, wato itacen jirgin ya qare ke nan sai ma'aikatan jirgin, wato Burga Boyi (Big Boy), da fayamasta (Fire Master), su sauka gefen hanya su kwashi busassun itatuwan Kwakwalagi xin sannan su ci gaba da tafiya, wato itacen Kwakwalagi kamar kwal (Coal) yake ke nan.

Irin wannan aiki da leburori bayin Allah suke yi, abu ne mai wuya qwarai idan aka yi la'akari da cewa wannan lokaci babu kayayyakin aiki irin na zamani, abin da suke amfani da shi, shi ne qarfin tuwo, gatari da adduna. Wannan aiki ne mai haxari babba, Allah kaxai ya san abubuwan da waxannan bayin Allah suke gani a cikin wannan qungurmin jejin.

Wannan mawuyacin aikin a hannun Malam Isa aka danqa shi, amma saboda aikace-aikacen gwamnatin Turawa sun yi yawa, sai aka ba da kwangilar aikin Kwakwalagi. Wanda aka bai wa kwangilar wannan mawuyacin aiki kuwa shi ne wani Bayarabe mutumin Ilori. Shi wannan mutumin ya yi aiki tuquru wajen tabbatar da zirga-zirgar jirgi daga Kaduna zuwa Zariya. Saboda saninsa da aka yi wajen aiki da leburori don nemo Kwakwalagi, har sunansa ya zama Kwakwalagi baki xaya.

Idan Mista Kwakwalagi, wato Bayaraben Ilori kuma xan kwangilar itacen jirgi, in ya kammala aikinsa, sai ya sanar da Malam Isa wanda zai lisafta yawan itatuwan da aka samu sannan a biya Mista Kwakwalagi kuxin aikinsa. Haka dai jama'a suka riqa shan baqar wuya wajen amfani da wannan jirgi. Shi wannan jirgi haka yake hanhai ba shi da rufi. Fasinjoji sai su zauna cikin rana ko kuma ruwa in lokacin damina ne. Da damina sai fasinjoji su riqa amfani da Kabido.

Harila-yau, a cikin shekarun 1912 zuwa 1935, babu isassun motocin aikace-aikacen da ya shafi ayyukan gwamnati. Abin da ake amfani da shi wajen kwaso, kayayyaki a wurare daban-daban, sai Alaro wato leburori. Da zarar kayayyakin gwamnati sun iso Kaduna Jamsin, ta hanyar Jirgi, to, Baturen da ya kawo waxannan kayayyaki ba zai danqa ga kowa ba sai Sarkin Alaro. Malam Isa ne zai sa hannu a kan ya karvi kayayyakin, sannan ya sa alaro su xauko waxannan kayayyaki. A wannan lokaci, sai ka gan su sun yi jerin gwano, wannan na bin wancan, suna xauke da kayayya ki iri-iri. A wannan lokaci sai ka ga waxannan

bayin Allah sun yi gumi sharkaf, suna tafiya tinkis-tinkis, wani lokaci kuma suna gudu suna sassarfa, har su kawo inda ake buqata. A nan ma sai Malam Isa ya bai wa Baturen karvar kaya wanda zai qirga kayayyakin, sannan ya sa hannu da cewa ya karva. Ana wannan abu ne domin a tafiyar da komai bisa gaskiya, don kuma a hana aukuwar rikici ta wajen vatar kayayyaki.

A shekarar 1913 an samu qaruwar ayyukan sufuri sosai saboda samun hanyar jirgi. An samu qarin dakon xaukar kaya a wannan lokaci. An xauki kayayyaki masu nauyin tan 51,185 a shekarar 1912, amma a shekarar 1913, 'yan dako wato alaro, sun xauki kaya mai nauyin tan 62,483. A wannan lokaci sai ana amfani da dawaki da shanu da raquma da jakuna wajen xaukar kaya zuwa waje mai nisa. Ga qididdiyar shekarar 1912 da 1913.[1]

	19	**19**	**Qar**	**Rag**
Alar	48,	59,	56	-
Da	12	11	-	16
Sha	31	33	28	-
Rak	-	11	113	-
Jaku	61	54	-	69

Duk da haka a wannan lokaci an fi amfani da alaro wajen xaukar kaya zuwa cikin gari da kewayen Kaduna. An samu raguwar amfani da dabbobi wajen xaukar kaya zuwa wuri mai nisa saboda samun hanyar mota da wasu motoci da Ma'aikatar Sufuri ta samu. Amma waxannan motocin an fi amfani da su wajen tafiye-tafiyen Gwamna. Akwai motar rangadi guda wadda ta ci nisan mil 2,052 tun fara aiki da ita. Ita kuma xaya motar tana zirga-zirga a gari ta ci mil 666 tun fara aiki da ita.

Tafiyar da aikin hedkwata sai da hanyoyi da motoci, saboda a kullum ana samun xaruruwan tan na kayayyakin gwamnati da na aikin gine-gine. Ana sauke su a tashar jirgin Maqera wato Kaduna Jamsin. Sarkin Alaro Malam Isa da *Political Officer* haqqinsu ne, su ga an kai kayayyaki wajen da ake buqatarsu a cikin lokaci.

Idan leburori sun gama aikace-aikacen wuni guda, sai a biya su sisi-sisi, wato kwabo shida (6d) shi kuma Malam Isa yana da kamashon 1d kana kowane lebura. Amma Ko da yake akwai xaruruwan leburori qarqashin Malam Isa, amma bai bar komai ba. Duk abubuwan da kuxaxen da ya samu wajen kulawa da leburorinsa suke komawa. Shi Malam Isa mutum ne karimi mai gaskiya da riqon amana, wanda don tsananin son leburorinsa (qabilu iri-iri), ba ya bambanta su da

[1] NAK/$AR_{2/2}$ Annual Colonial Reports/xziii, 1911

'ya'yansa. Wajen Malam Isa da xansa da leburansa duk xaya suke. Haqqin kowane mutum na kowace qabila dai-dai yake a wajensa.

Saboda shaquwar da leburori suka yi da Malam Isa sai ya zama a lokuta da yawa shi ne ke wakilcin xaura masu aure, a duk lokacin da suka buqace shi. Amince masa da leburori suka yi, ya kawo cikas wajen kafuwar dokar hana yawon dare. Don kuwa duk wanda 'yan Sanda suka kama da dare sai ya ce da su a gidan Malam Isa yake, sai su kuma su sake shi. Turawan mulki na matuqar sauraron sa domin wanda yake shi ne shugaban xaruruwan leburori wato *Labour Leader*, shi ne ya riqe ragamar tafiyar da al'amarin gari.[1]

Saboda karimcin Malam Isa, gaskiya da riqon amanarsa. ya sa kowa da kowa, yaro da babba sun san gidan Sarkin Alaro. Daga garuruwa na kusa da na nesa ya kan samu wasiqu kamar haka, "zuwa ga Sarkin Alaro, saboda mun ji labarin gaskiyarka da riqon amana, don haka ga kayayyakinmu nan da iyalanmu mun turo su wajenka kafin mu taho. " Saboda saukar baqi yana xaya daga cikin aikinsa, domin haka in ya samu saqo daga nesa ya kan kula da abubuwa uku (i) Haqqin wanda ya aiko da amanarsa (ii) Haqqin abin amanar (iii) Haqqin hukuma. Allah Ya bai wa Malam Isa, basira da hakurin riqe haqqoqin jama'a.[2]

Wata rana an yi baqon wani Bature wanda ya zo ya ga leburori na aiki, amma ga wani dattijo can a zaune. Shi wannan bature, sai ya ce da dattijon, "yaya ba ya xaukar kaya? " Sai wannan dattijo ya yi murmushi ya ce da bature, "kaya kake so in xauka? " Ko da yake leburori suna cewa, da Baturen da yanatsu, wannan dattijo shi ne Malam Isa Sarkin Alaro, amma ba su yi aune ba, sai suka ga Malam Isa ya dumfari wani qaton dutse wanda qarti *arba'in* ba yadda za su yi da shi, suka ga ya yi xan gammo ya durqusa wajen wannan dutse, ya ce, "Bismillahi. " Ya yi sama da dutsen ya xora a kansa tamkar ya xauki karmami.

Kowa sai mamakin wannan abin al'ajabi yake yi ga Malam Isa xauke da mulmulellen dutse ya nufo gidansa a layin *Prince Edward*. Yana tafe yana rangwaxa tamkar bai xauki komai ba, jama'ar gari da makaxa da 'yan algaita sai suka yi wo kansa, suka rako shi gidansa.[3] Allah Ya yi wa Malam Isa rasuwa a cikin shekarar 1945, ya bar 'ya'ya guda huxu, Amina (Goshi), da Muhammadu Labaran, Yusufu da kuma Musa.

---

1 Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 15 ga Mayu 1984.

2 *Ibid*.

3 *Ibid*.

Mista Thompson

"Gwaxayi ba saranka ba ja!"

Mista Thompson baqar fatar Saliyo ne wanda ya biyo Turawa zuwa Arewacin Nijeriya a cikin shekarar 1900. An haife shi a cikin shekarar 1837 a *Freetown* ta qasar Saliyo. A wannan gari ne ya yi karatunsa har ya yi ilimi mai zurfi ta wajen fannin lauya. Yana xaya daga cikin manyan shugabannin da suka kafa garin Dungurun.

Mista Thompson shi mutum ne mai kwarjini da son jama'a da barkwanci, ya kuma iya zama da su. Allah Ya ba shi hazaqa, da iya magana, har wani loto ma in ya yi magana sai ka ji kamar ka xaura ta a wuya don kyawunta da dacewarta. Saboda irin waxannan halayensa ne, cikin xan qaramin lokaci sai ya bunqasa ya zama sananne a duk qasashen Hausa.

Wajen fanninsa kuwa na wajen aikin lauya, ba shi da na biyu domin ko Turawan Mulkin Mallaka shakkarsa suke yi. A cikin shekarar 1924 shi ne mataimakin babban akawun da ke aiki a Sakatariyar da ke Kaduna. Ya samu shekaru da dama yana yi wa Turawan mulki aiki kafin ya yi ritaya. Saboda babban taimakon da wannan bawan Allah Ya bayar wajen tafiyar da aikace-aikacen Arewacin Nijeriya, an ba shi lambar yabo a lokacin da ya yi ritaya.

Bayan ritayar Mista *Thompson* daga aikin gwamnatin Turawan mulki, sai ya koma lauya mai zaman kansa. A wannan lokaci ne fa, duk manyan shugabanni da attajirai su kan zo wajensa domin samun shawarwari da neman yadda za su sami galabar shari'a. Saboda haziqancinsa da qwarewarsa wajen aikin lauya, da siyasar iya zama da jama'a shi ya sa ma ake yi masa kirari da, "Gwaxayi ba saranka ba ja. " Wato ba rikici da Mista *Thompson* ke da wuya ba, a ci galabar rikicin da shi, shi ne abu mawuyaci.

Manya-manyan mutanen wannan zamani su kan zo wajensa saboda neman qarin ilimin fannin Siyasa ko na shari'a. A wannan lokaci, Alhaji Abubakar Imam ya karanci fannoni da dama wajen Mista *Thompson* wanda ya zama babban abokinsa. Bunqasar Mista *Thompson* ta yi nisa qwarai da gaske domin har Sarakunan Hausa sun ba shi aure. Sarakunan da suka ba shi aure a wannan zamani su ne: Sarkin Zazzau Alu, Sarkin Kano Abdullahi da Shehun Barno Sanda Kori, Shi kullen matansa yake yi a wannan zamani.[1]

Mista *Thompson* ya musulunta a cikin wajen shekarar 1933, a lokacin Sarkin Zazzau Ibrahim, ya kuma canja sunansa zuwa Malam Isa *Thompson*. Ya shiga neman takarar Sarautar Sabon Garin Doka a wannan lokaci. Malam Isa *Thompson* ya rasu ya bar 'ya'ya mata uku, Anini da Ladi da kuma Laure.

---

[1] Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 20 ga Mayu 1984.

Sarkin Pawa Muhammadu

"Makasau Kuren Gwamna "

Sarkin Pawa Muhammadu an haife shi a garin Tere a Gundumar Rano ta qasar Kano. Yana xaya daga cikin mazauna Dungurun a lokacin da aka kafata. A wannan gari ne ya samu Sarautar Pawa, inda yake jigilar kwangilar kai nama ga sojoji, 'yan Sanda da sauran ma'aikatu da asibiti.

Arziqin Sarkin Pawa Muhammadu ya daxa havaka matuqa a garin Kaduna saboda qaruwar sojoji da ma'aikata a wannan gari. Allah Ya yi wa wannan mutum kyauta da son jama'a. A lokacinsa duk wani sha'anin da ya buqaci taimako, to, Sarkin Pawa ne kan gaba. Misali idan a cikin wata guda za a yi bikin suna xari, to, kuxin raguna hamsin daga cikin xari, Sarkin Pawa ne ya taimaka. Haka kuma wajen xaurin aure, hamsin bisa xari shi ke xaukar jigilarsu ta wajen kayan xaurin aure da biki. Ban da sha'anin suna da xaurin aure, wajen jana'iza kuwa Sarkin Pawa Muhammadu ke taimakawa wajen aiko da likkafani a kusan duk inda aka ce an yi rashi.

Wajen taimakon talakawa kuwa, kusan a ce ya fi kowa a zamaninsa a garin Kaduna, Domin Sarki Muhammadu ya yi nisa. Wannan Sarkin Pawa ya fahimci yadda rayuwa take, da yadda Allah Ya bambanta jama'arsa wasu ya yi su talakawa, wasu kuma ya yi su masu arziqi, sannan ya buqaci masu arziqi da su taimaka wa talakawa don Girmansa. Saboda haka Sarkin Pawa ya umarci mahautansa da a kowace rana su riqa yanka sa xan bana bakwai domin talakawa kada su sha miya lami. A wannan lokaci sa xan bana bakwai kuxinsa bai wuce fam uku da sulai hudu (£3.4s.0d). A kullum safiya, sai mahauta sun fito da sa sun yanka suna jiran bayin Allah da su zo a yanka masu naman miya. Da misalin qarfe tara zuwa goma na safiya sai ka ga jama'a sun yi layi kowa na murmushi yana faxin inda yake so a yanko masa. Waxanda suka karvi na su, za ka ga sun fito suna masu annashuwa suna masu gode wa Allah da ya azurta su da Sarkin Pawa Muhammadu. Haka aka riqa yanka mulmulellensa, a kowace rana, don a rabawa talakawa naman miya!

Wata rana Sarkin Pawa ya je Kwata, sai ya ga mahauta na korar angulaye, ba domin komai ba sai don sun zo cin yaxi. Wannan abu da ya gani sai ya tayar masa da hankali, ya ga cewa ga wasu halittun Ubangiji suna gani ake yanka shanu, suna kuma gani ake kwasar naman amma ga shi cin yaxi ma ya gagare su. Saboda wannan dalili, sai Sarkin Pawa ya gargaxi mahauta da kada su riqa korar angulaye, abin da za su yi shi ne a kullum safiya su yanka sa, su fexe shi su cire qashin su kuma yanka tsokar naman gunduwa-gunduwa sannan su watsa wa angulaye su ci, ba domin komai ba sai don girman Allah.[1]

---

[1] Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 20 ga Mayu 1984.

Mutanen Kaduna a wannan lokaci sun ga abin mamaki domin a kullum sai su ga an fito da shanu biyu, xaya an yanke wa talakawan gari, xaya kuma an yanka wa angulaye. Da safiya ta yi sai ka ga angulaye sun yi cirko-cirko kan runfuna suna jiran a yi masu yanka. Wajen misalin qarfe 10 na safe sai ka ga nan ga jama'a sun yi layi kowa na karvar naman miya. Nesa da su kuma cincirindon angulaye ne sun duqufa suna cin jar tsokar nama. Haka aka riqa yi har nisan zamani.

Wajen taimakon mahauta 'yan uwansa kuwa, Sarkin Pawa nan ma ya yi nisa. Da mahauci ya zo neman jari sai ya ce a tafi da shi garken shanu don ya zavi san da yake buqata. Idan ya sayar da nama ya kawo kuxin. Wannan abu ya taimaka wa mahauta matuqa. Da yawa daga cikinsu sun yi arziqi ta hanyar Sarkin Pawa Muhammadu.

A wannan zamani Sarkin Pawa, ya ba da umarni cewa kada a bar mahaukata su riqa yawo tsirara ko kuma cikin muguwar kama. Don haka ne aka ware maqudan kuxaxe wajen sayen tufafi na maza da mata. Jama'arsa yawo suke yi layi-layi, kwararo-kwararo suna neman mahaukata. Da ganin mahaukaci sai su kama shi, su saka masa sutura sannan a sake shi ya tafi. Sarkin Pawa Muhammadu ya ce ai mahaukata ma gajiyayyu ne, saboda haka sai a taimaka masu. Ko da yake babu gidan mahaukata da aka tanada domin ba su magani, amma ba a barinsu suna gantali a gari kuma cikin muguwar kama. Taimakon Sarkin Pawa Muhammadu bai tsallake su ba don suna tavavvu.

Roqon Allan 'yan Fursuna a wannan lokaci, shi ne Allah Ya sa su ci karo da Sarkin Pawa Muhammadu a duk lokacin da suka fito aikin fursuna. Idan 'yan fursunoni suka ci karo da Sarkin Pawa a gari, sai ya xaga hannu, ya nuna wasu rukuni sannan ya ce "Daga nan ku tafi a ba ku rigunanku na 'yanta ku. " Waxanda Sarkin ya yi masu afuwa sai a koma da su, suna farin ciki suna masu barazana sannan a ba su rigunansu a kuma sallame su su tafi garuruwansu ko da lokacin sallamar su bai yi ba. Wannan qasaitaccen, wato Sarkin Pawa, Turawa masu kula da fursunoni, dole su bi umarninsa saboda babbar dangantakarsa da Gwamna Lugga. Domin kwarjininsa sun shaqu da Gwamna Lugga tun a Dungurun, don haka ma ne ake masa take da "Makasau Kuren Gwamna" saboda wannan qasaitarsa ne, fursunoni ke roqon Allah Ya sa su ci karo da shi, ko sa samu afuwa wato *Amnesty*!

Arziqin 'Makasau Kuren Gwamna', sai havaka yake yi, ya mallaki garken shanu wajen goma waxanda ake masa kiwo a wurare da dama. An ce idan shanunsa suka fito kiwo sai a yi tafiyar wajen kilomita guda ba su tsinke ba. Kullum sai haihuwa suke yi, arziqinsa kuma sai gaba yake yi.

Sarkin Pawa Muhammadu shi ne mutum na biyu wanda ya fara mallakar motar shiga a cikin Garin Kaduna. Wadda ta fara mallakar mota ita ce Kashi Bida, wata mace Bakanuwa 'yar kwangila da kamfanin *UAC*. Daga ita sai 'Makasau

Kuren Gwamna,' wanda ya sayi motar Muhammadu Tambari, a lokacin da Turawa za su wuce da Sarkin zuwa garin Wukari.[1]

A tarihin Kaduna, akwai mazaje da Allah Ya yi wa arziqi tare da baiwar kyauta da son jama'a. Daga Sarkin Pawa Muhammadu, sai Malam Aminu IIori wanda shi ma wani ne wajen kyauta. Daga shi sai wakilin Kaduna Alhaji Audu Kwangila wanda shi ma a lokacinsa ya kyautata wa jama'a.

Allah Ya yi wa Sarkin Pawa Muhammadu rasuwa, ya kuma bar 'ya'ya huxu, su ne: Mamuda, da Halima, da Kulu da Ibrahim. Allah Ya ji qansa, amin.

Liman Malam Jafaru

"Magatakardar Gwamna "

Liman Malam Jafaru, xan Alhaji Abubakar Baqo Gaji, an haife shi a Darma ta Katsina a cikin shekarar 1862. Alhaji Abubakar xan wani mashahurin Malami ne mai suna Malam Muhammadu da ke Birnin Kogo a qasar Faskari.

Allah Ya yi wa Alhaji Abubakar albarkar bautar iyaye don neman albarkarsu. Saboda wannan kyakkyawar xabi'a tasa, sai mahaifinsa Malam Muhammadu ya sa masa albarka ya kuma umarce shi da ya tafi makaranta neman. Jin wannan, sai ya shiga tafiye-tafiyen garuruwa daban-daban domin bixar. Ya zauna a garuruwan Agadas, Sakkwato, Gwandu, Zariya da Kano neman karatu. A cikin wannan lokaci ne, ya tafi aikin Hajji, lokacin ana tafiya a qasa.

Da Allah Ya ba kakan Jafaru ximbin ilimi, sai ya komo gida Katsina inda ya zauna a Unguwar Darma. A Katsina ne Allah Ya azurta Alhaji Abubakar da 'ya'ya, a cikinsu har da Jafaru. A unguwar Darma ya buxe makaranta inda yake ba da karatu, a kan zo wannan makaranta daga nesa wajensa domin neman ilimi.

Shi ma Alhaji Abubakar sai ya ba 'ya'yansa kyakkyawar tarbiyya, ya kuma kwaxaitar da su bixar ilimi, saboda haka ne suka duqufa wajen almajirci. Tun yana yaro, Allah Ya yi wa Jafaru haziqanci tare da bin iyaye, don haka bisa umarnin mahaifinsa sai ya baro gida, ya fito neman ilimi. Malam Jafaru ya yi karatunsa wurin manya-manyan Malamai a qasar Gwandu, a wannan garin ne ya yi auren fari.

Bayan da Malam Jafaru ya samu karatu, sai ya dawo Unguwar Darma a Katsina wajen mahaifinsa. Bayan rasuwar Alhaji Abubakar, sai Malam Jafaru da 'yan uwansa suka ci gaba da tafiyar da sha'anin makaranta. Jama'a daga nisan duniya na zuwa xaukar karatu wajensu.

A lokacin mulkin Turawa, 'yar tangarxa ta auku tsakanin wansu Malam Jafaru da Hukuma, wannan abu ya sa suka watse suka bar Katsina. Malam Jafaru da ya baro gida sai ya taho Lakwaja, a wannan lokaci akwai Sarakunan Arewa a

[1] Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 15 ga Mayu 1984

wannan gari waxanda Turawa suka tuve. A garin Lakwaja, ne Sarkin Katsina Muhammadu Dikko ya haqu da Malam Jafaru, har Sarkin ya buqace shi da ya koma gida Katsina, don ya ba shi alqalanci amma wannan abu bai yiwu ba.

Daga garin Lakwaja, sai ya koma hedkwatar Arewa Dungurun, domin a lokacin tana tashe, akwai 'yan Arewa maqil a cikinta. A wannan gari ne ya samu ci gaba ya riqe babban muqamin magatakardar gwamnan Arewa baki xaya, Gwamna Lugga. Idan Gwamna Lugga ya buqaci rubuta wasiqa zuwa ga ko Sarakunan Hausa, to, Liman Jafaru ne ke rubuta masa, haka kuma idan suka rubuto wa gwamnan, to, Malam Jafaru ne zai karanta masa cikin Arabi ko Ajami. Saboda wannan muqami nasa, sai ya samu kyakkyawan dangantaka da Turawan mulki tare da Sarakunan wannan lokaci.

Da aka dawo Kaduna da zama, sai Liman Jafaru ya zama shi ne limamin farko a wannan sabuwar hedkwatar. Yana limancin sallah a babban Masallacin Juma'a da ke layin Kano a wannan zamani. Koda aka kafa kotun *Station Magestrate* a Kaduna, Liman Jafaru ne aka danqa wa bincike da gabatar da bayanin mai qara a wannan kotu. Saboda bunqasar Kaduna, sai ayyuka suka yi wa wannan shaharraren mutum yawa, don haka ne bai samu sukunin ba da karatu ba, sai dai limancin sallar juma'a a babban masallacin Kaduna da ke layin Kano (Kano Road).

Wannan mashahurin limami, magatakardar Gwamna Lugga ya bunqasa sosai da sosai a cikin qasashen Hausa. Malamai da Alarammomi sun taimaka wa gwanatin Gwamna Lugga sosai, don haka ne ya samu jin daxin mulkin Arewa. Alarammomi ne suka fara riqe ayyukan gwamnati a Arewa, kamar muqamin scribe wato magatakarda, da *cashier* ma'aji da wasu muqamain gw3amnati daban-daban. Liman Malam Jafaru ya rasu ya bar 'ya'ya bakwai:- Sule, da Ibrahim, da Aqilu, da Abdullahi, da Abdulwahidi, da Maimunatu da Halimatu. Allah Ya ji qansa amin.

Malam Attahiru

Tinjimin Malami Uban Tijjani, kan da sarauta, cikin da karatu, hannun da rubutu, qafar da taqama, zuciyar da kyauta, bakin da hadisai.

Malam Attahiru ya taho daga fadar Sarkin Kano a wajen shekarar 1927, inda ya komo da zama a garin Kaduna. Zaman wannan Malami a wannan gari ya taimaka qwarai wajen bunqasarsa da tafiyar da mulkin Turawa ta fannin shugabanci.

Yana xaya daga cikin qusoshin gwamnatin wannan lokaci a matsayinsa na Shugaban Malamai da Mai bada shawarwari ga shugabannin mulki. Wajen jama'ar gari kuwa, Malam Attahiru ya yi taimako wajen koyar da jama'a, domin

ya yi nisa a fannoni da dama. Shi mutum ne Malami mataffanoni wanda Allah Ya albarkata da ximbin sanin hadisan Annabi Muhammadu (Sallallahu Alaihi Wassalam) da tarihi, da hisabi da dai sauran fannoni.

Allah Ya yi wa Malamin Muhibba da kwarjini da iya tafiyar da mulki. Shi mutum ne karimi ga son jama'a, don duk inda ka ga babban Malami ka ga Malamai na biye da shi.

KASHI NA BIYAR

Shari'a da Dokokin Gari

A lokacin da Turawa suka shigo lardin Zazzau sun tarar da akwai kotuna iri uku a Zariya: Kotun Sarki, da Kotun Alqali da Kotun Salanke. Waxannan Kotunan sun samo asali ne lokacin Sarakunan Have. Fulani da suka kafa mulkinsu sun ci gaba da aiki da waxannan kotuna. Alqali shi ne Babban mai zartar da hukunci, wato *Chief Justice*, Salanke shi ne Matafiyi Mai Sharia wato *Travelling Judge*. Shi ke bin Sarki a lokacin rangadi. Amma Alqali a zamanin Fulani na iya sauya hukuncin Salanke.

Sarkin ba shi da ikon sauya hukuncin Alqali, sai a lumurra da suka shafi rikice-rikice a kan iyakar qasa da makamantansu wanda Sarki da majalisarsa ka iya zartar da hukunci. Haka saboda 'yan Doka da 'yan Sanda na qarqashin ikon Sarki, shi ke ganin an zartar da hukuncin Alqali a kan kowa. Shi ke da ikon naxa Alqali da Salanake, har iya rayuwarsu sai dai in doka ta cire su saboda wasu laiffuka. Da zuwan Turawa sai suka yi wa wannan tsari gyaran fuska.

Bayan jama'a sun zauna a Kaduna kuma gari na ci gaba da havaka, saboda halin yau da gobe da kuma halayyar mutane ta wajen sata, faxa da rikice-rikice dai, sun jawo dole sai an buqaci Alqali Dungurawa, mazaunan farko, idan maganar shari'a ta kama, sai su tafi garin Kangiwa wato Kinkinau su gurfana wajen Alqali Malam Tsoho. Shi Alqalin wannan kotu. Alqali ne mai ximbin sanin fannin shari'a. Yana da muftai har uku: Malam Halilu, da Malam Haruna, da Malam Awaisu dukkansu daga Zariya ake naxo su.

A wannan lokaci sai aka xauke Malam Halilu a ka yi masa alqalancin garin Zunta, don haka sai aka kawo wani muftin daga Zariya mai suna Malam Hurdi domin ya maye gurbinsa. Amma daga bisani sai aka xauke mufti Malam Hurdi zuwa garin Kauru inda aka naxa shi Alqali. Saboda haka sai aka kawo Malam Ilu daga Zariya ya zama muftin Alqalin Kinkinau (Kangiwa) Malam Tsoho Ibrahim.

Duk a wannan lokaci mai tsawo ba inda ake yin shari'ar Alqali a Kaduna, in ba garin Kangiwa ba. Ita wannan kotu an maida ita matsayin mai daraja ta Huxu ko 'Grade D,' a ranar 21-8-1913. Bayan da aka kafa garin Tudun-Wada a cikin shekarar 1924, Malam Tsoho Ibrahim ya yi ritaya sai aka xauko Malam Halilu aka maida shi mufti a Kagarko Malam Hurdi sai ya dawo alqalanci a Tudun-Wada Kaduna.

Amma yadda ake zartar da hukunce-hukunce na alqalan Arewa ba zai yiwu a garin Kaduna ba kamar yadda ake yi a sauran garuruwan Arewa. Saboda gari ne mai qabilu iri-iri kuma mabiya addinai daban-daban. Sa'annan ga Turawan mulki

sun kawo na su salon sharia. A dalilin haka ne aka kafa kotu ta musamman da ake kira kotun *Station Magestrate*.

Kotun *Station Magistrate*

Domin a qarawa waxannan kotuna qarfi da kuma a ga cewa yankunan da ke qarqashin mulkin En'e suna samun hukunci a kotunan Alqalai masu daraja ta Huxu 'D' da suke a garuruwan Kangiwa (Kinkinau) da Rigachikum, sai aka naxa Mista M.C. Greene, a matsayin Jami'i mai lura da harkar siyasa da ya sa ido akan su. Shi ne yafara riqe muqamin. A shekarar 1915, sai a ka turo Mista Macgregor da ya riqe wannan muqami.

Haka kuma sai aka buqaci Alqalan waxannan kotuna da su riqa zuwa kotun *Station Magestrate* domin su saurari qararraki da suka shafi Al'adu da Addinin jama'a, a kowane mako. Kamar qarar da ta shafi aure da saki da rabon gado.

A cikin shekarar 1916, sai aka kafa kotu ta musamman mai suna "Kotun *Station Magestrate* " a cikin Kaduna "Township. " Wannan kotu tana qarqashin shugaba wanda ake kira *Station Magestrate*. Wani lokaci, shi *Station Magestrate* kwamishinan 'yan Sanda ne ke riqe da muqamai guda biyu - aikin kula da 'yan Sanda da kuma aikin kotu. An kafa wannan kotu domin ta ji koke-koken jama'a ta kuma kula da dokokin gari.[1]

Aikin *Station Magestrate* yana da yawa. Shina zai tanadar kuxaxen shiga da lissafa yadda za a kashe waxannan kuxaxe don gyaran garin Kaduna. Ana samun kuxin shiga wato "Revenue, " ta wajen kuxin qarar kotu da kuxaxen lasisinan motoci da basukuri da kuxin runfunan kasuwa, da kuxin fulotin gidaje da na haya da dai sauransu.

Kowane *Station Magestrate* zai yi aiki na tsawon watanni goma sha-biyu, sannan ya rubuta wa Gwamna rahoton duk abubuwan da suka faru a cikin garin, da kuma yadda al'amuran jama'a ke tafiya kafin wani baturen ya maye gurbinsa.

Saboda *Station Magestrate* ya samu sauqin tafiyar da ayyukansa, sai aka naxa shugabannin garin guda huxu wato 'yan Majalisar Gari; 'yan wannan qungiyar Majalisar su ne: "Sarkin Hausawa Babale, da Sarkin Nufawa Maliki sai kuma Sarkin Yarbawa Balogun, da Malam Aminu Bayarabe. Su waxannan shugabanni sun taimaka qwarai da gaske wajen tafiyar da hukunce-hukuncen gari. Shi Malam Aminu Bayaraben Ilori ne, mai aikin karvar harajin fulotai da kuxaxen haya wato, *Rate and Rent Collector*, amma daga bisani an zargi Malam Aminu Ilori da xaukar kansa tamkar Sarkin Kaduna. Shi qasaitaccen mutum ne wanda yake riqe da muqamin mai karvar haraji sannan yana aikin kwangilar Fidaburdi. Saboda

[1] *Zaria Provincial Gazetteer* 1916, shafi na 36

haka sai aka cire shi a mai karvar kuxi, amma an bar shi da ya ci gaba da zama xan Majalisar gari.[1]

Kotun shari'a

Saboda ayyukan *Station Magestrate* sun yi yawan sosai, saboda haka sai aka kafa xakin shari'a a cikin Sabon Gari. Ita wannan kotun sai ta shiga aikin jin qararrakin jama'ar gari, saboda haka sai mutane suka daina zuwa Kangiwa domin shari'a. Ana hukunta masu laifuka sannan kuma wannan kotu na taimakawa wajen samun kuxin shiga.

Tun kafin a kafa wannan kotun shari'a, aikin *Station Magestrate* ne hukunta duk wani mai laifi a Kaduna da kuma sauran garuruwa a Arewa. Ita wannan Magistrate tana matsayin Babbar Kotu ke nan domin kuwa ana jin kowane irin qararrakin jama'a. Misali idan an zalunci wani mutum a wata qasa kuma ya kawo qara a kotun *Station Magestrate* da ke Kaduna, sai ma'aikatan wannan kotu su shiga neman bayani a gare shi. Ita wannan *Magistrate Court* ta tanadi xakunan saukar baqi masu qara da abinci domin masu tahowa daga nisan duniya. Saboda su kan zo a jigace, a wani lokaci ma ba a cikin hayyacinsu ba.

Da isowar mai qara sai ya shiga kaxa qararrawa yana cewa na kawo qara na kawo qara! Waxansunsu ma har birgimasu kan yi domin baturen mai shari'a ya tausaya masu. To, wanda ya zo a jigace sai a ba shi abinci yaci, sannan a kai shi masauki, kashegari in ya dawo cikin hayyacinsa, sai ma'aikatan shari'a su shiga neman bayani. Liman Malam Jafaru wanda shi ne Magatakardar Gwamna shi ke rubuta bayanin mai qara da ajami, sannan ya bayyana wa "*Station Magestrate*. " Nan da nan sai mai shari'a ya aika da 'yan bincike domin su tafi garin da aka buqacesu su kuma binciki yadda ainihin al'amarin yake kafin su taho da wanda ake qara xin. Saboda haka kafin nan da kwana uku an gama binciken an kuma zartar da hukunci, akan kowane ne aka samu da laifi sai a hukunta shi kamar yadda shari'a ta buqata.[2]

Kafa kotun shari'a a Sabon Garin Doka a cikin shekarar 1920, ya rage wa *Station Magestrate* aikace-aikacen shari'a da yawa. In har shari'a ta zo gare shi, to, ta fi qarfin Alqali ke nan, sai Kotun Qoli wadda take qarqashin *Station Magestrate*. Alqalan farko waxanda suka fara shari'a a cikin Sabon Kotun Garin Doka, su ne Alqali M. Sa'idu sai Alqali Malam Lukumanu. Bayan waxannan Alqalai, sauran da suka yi alqalancin su ne; Alqali Malam Sani daga shi sai Alqali Malam Shu'aibu Banufe. Duk da kotunan Alqali da *Station Magestrate* sai da harkar shari'a ta hargitse a Kaduna. Saboda bambancin da ke akwai a tsakanin

---

[1] Annual Report 1920: *Office of the Station Magistrate*

[2] Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 25 ga Mayu 1984.

jama'a ta addini da al'ada. A dalilin haka ne aka kafa wata kotu mai suna "mixed court. "

Kotun *Mixed Cour*t

Ita wannan kotu ta Haxin Gambiza, ta samo asali ne tun cikin shekarar 1930. Garin Kaduna cike yake da jama'a qabilu iri-iri masu addinai da al'adu waxanda suka bambanta da juna. Da farko dai jama'ar gari na qarqashin Dokar Kotun Qoli ko *Supreme Court* wadda ita ma take qarqashin *Station Magestrate*. Amma saboda qabilu daban-daban waxanda galibinsu mutanen kudancin Nijeriya da ke zaune a Sabon Garin Doka, sai aka ga hukuncin Alqalai bai dace da su ba saboda bambancin al'adu, da addini.

Yadda al'adu kan bambanta kuwa wuri uku ne: (i) Aure (ii) Gado (iii) Jayayyar 'ya'ya. Amma sauran laifuka kamar sata, faxa da bashi duk xaya ne. An kafa *Mixed Court* a shekarar 1932 a matsayin kotu mai daraja ta uku ko 'Grade C'. Ita wannan kotun da aka kafa a Kaduna, tana jin qararraki ne tsakanin Musulmi da waxanda ba Musulmi ba, waxanda suke zaune a Kaduna da sauran sassan Arewa. Su Musulmi sai a yi masu hukunci bisa shari'ar da Alqali ya zartar, su kuma waxanda ba Musulmi ba sai a hukunta su da al'adunsu. Mutanen da ke kawo qararraki sun qunshi mutanen lardin Igabi cikin Tudun-Wada da Sabon Garin Doka.

Alqalin wannan kotu yana da muftai har guda uku waxanda suke shugabannin Yarbawa da Ibo, su waxannan su ke ba da fatawa wajen shari'ar mutanensu bisa al'adunsu. Su waxannan muftan masana ne bisa shari'a da al'adu. Na ukun, shi ne Malam Bahaushe masanin shari'a. Duk waxannan masu shari'ar, suna qarqashin shugaban kotun baki xaya. Da farko dai shugaban kotun *Mixed-court*, shi ne Hakimin Igabi. Ita wannan kotu ta taimaka sosai wajen tafiyar da shari'a ta, kawo zaman lafiya da lumana a cikin Sabon Garin Doka da kewaye.

Wannan kotu na da ikon jin qararrakin jama'a daga qauyukan da ke kewaye da Kaduna da Sabon gari da gundumomin Igabi da Cikum. Tana sauraron qararraki ne tsakanin Musulmi da Kirista da sauran qabilu mabiya aqidunsu da suka bambanta da juna.

Kowace qabila tana da hanyar zartar da hukunci wanda ta kevanta da shi saboda tasirin addini da al'ada. Hukunci in zai karbu ga qabilu ya kamata ya dace da halaye da xabi'unsu. Saboda haka ita kotun za ta kawo maslaha wajen zartar da hukunci tsakanin qabilu.

Kotun za ta ba da dama ga qabilu, da su zartar da hukunci kamar yadda ya dace da al'adunsu da xabi'unsu, amma kuma ba ta yadda zai zarce tsarin babban kotu ba. Amma ta fi dacewa da jin qararrakin wanda ba za akai ga kotun Alqali ba. Ita wannan kotun haxin gambiza ba za ta riqa samun katsalanda ba. Mutane da dama ba su saba da tsarin En'e ba, saboda haka kotun gambiza ta dace da su.

Wasu kuma sun fi sabawa da kotun *Station Magestrate* don wannan kotu ta amsu garesu.

Ko da yake kotun ba ta samu karvuwa daga jama'a ba, amma 'yan Kudu da yawa sun gamsu da ita, har ma ji su ke sun fi 'yan garin wayewa da, 'yanga-ranci. Wasu kuma fata suke yi da, cewa kafa wannan kotu shi ne takin farko wajen samun matsayin maida Kaduna Babban birnin ko *Municipal Status* ga garin Kaduna.

A shekarar 1935 kotun ta samu qarin sabon salon jin qararraki tsakanin Musulmi da Kirista, wanda daga qarshe aka kafa ma ta majalisar ba da shawara. Amma da aka cire sabon garin Kaduna, aka maida ita qarqashin En'e ta Zariya a watan Yuni na shekarar 1940, sai kotun ta qara samun sauye-sauye. Shugaban kotu ya zama yana da mambobi guda biyu na dindindin masu karvar albashi da sauran mambobin da 'yan majalisa masu ba da shawara ta zava, waxanda za a biyasu hakkinsu a kowane zama. A wannan shirin akwai mambobin dindindin guda uku masu albashi kuma suna matsayin muhutai.

A shekarar 1940 aka sake tsarin wannan kotu bayan da Sabon Garin Doka ya koma qarqashin mulkin En'e ta Zariya. Ta qunshi shugaba da mambobi guda uku waxanda majalisar ba da shawara ta zava. A kwai memba wanda Sarki zai naxa. Dukkansu suna da albashi.

Kafin a sake mata sabon tsari, an samu jayayya daga wasu mutane waxanda suke baqi 'yan wata jiha wato 'yan Kudu. Sun yi qorafi da cewa suna tsoron kada su rasa yancinsu wajen sharia da suna tsoron 'yandoka sannan kuma suna gudun ka da su rasa haqqin wakilci a Majalisar wannan kotu.

Malam Baqo ya zama shugaban wannan kotu an naxa shi a watan Mayu na shekarar 1940. Yana muhutai waqanda suka haxa Mista Samuel Bayarabe, da Mista Odili Ibo da Malam Abubakar a qarqashinsa. A hankali sai farin jinin kotun ke qaruwa. Saboda haka sai Mista MacCallum na Ofishin Qaramar Hukumar Mulki ya aikawa shugabanni saqo kamar haka:

"Ko shakka babu dalilin da ya sa 'Mixed Court' ta samu farin jini gaya, saboda Malam Baqo, shugaban wannan kotu mutumne mai gaskiya. Dukkan sashen qabilu sun amince ma sa suna kuma girmamashi. Haka ma mambobin kotun ana ganin su da girma."[1]

Ko shakka babu, aikace-aikacen wannan abu ne mai wuyar gaske. Malam Baqo ya samu kan sa a tsaka mai wuya. Saboda idan za a hukumta mutum da al'adarsa, to Musulmi za a qwara saboda shi ba shi da wata al'ada in ba shari'ar

[1] C.35/111/16/6/1952

musulumci ba. Turawa da 'yan Kudu ba abin da suke qi kamar wannan shari'a. A wancan zamani har ya zuwa yanzu, xan Kudu bai xauki xan Arewa komai ba. Saboda homa da feleqensu har sun wuce gona da iri, wajen nunawa da rungumar al'adun Turawa.

A matsayinsu na "Baqaqen Turawa, " suna ganin sun fi qarfin 'yan Arewa a komai, qaskanci ne su tafi gun Alqali. Ko da yake sun fi son kotun *Station Magestrate*, amma ita kuma Musulmi na qyamarta don ba ruwanta da musulunci. To idan rikici ya faru tsakanin xan Arewa Musulmi da xan Kudu Kirista ko da xan Arewa wanda ba Musulmi ba, sai lamarin ya harqe.

Ita *Mixed Court* sai ana ganin za ta ba da mafita, idan aka koma hukunci da al'adu, Musulmi kuma al'adarsa shari'ar Musulmi. Wani lokaci kam, tilas a rasa mafita a wannan kotu, a koma amfani da wayo da dabaru, wajen kawo sulhu ko hukunci a tsakanin masu qara. Duk yadda ake yi babu mafita ga Musulmi a *Mixed Court* ko a *Station Magestrate*. Amma cikin waxannan biyun nan, *Mixed Court* ta fi tsahirta wa Musulmi.

Duk da rikice-rikicen da suka dabaibaye wannan kotu, ta yi rawar gani a wancan lokaci. Saboda haka ne shugabanta ya samu yabo daga Turawan mulki da sauran jama'ar gari.

A wajen *qararrakin* jama'a kuwa, an fi samun iri huxu manya su ne: sata, da cin zarafi, da laifukan da suka shafi karya dokokin En'e, da ba shi. Kaxan ake samun qararraki kan aure, ba a kuma samu akan gado ba ko jayayyar ya'ya.

Haka kuma ba a tuntuvar muhutai. A kotun Kaduna ma ba a nemi mahuti ba ko da sau xaya a shekarar da ta gabata. Shugaban *Mixed Court* ya yi nuni da cewa an fi samun qararrakin bashi tsakanin Musulmi da wanda ba Musulmi ba. A na kuma zartar da hukunci ba da shari'ar musulunci ba.

Amma da *qorafe-qorafe*n jama'a suka yi yawa, sai a shekarar 1949 Sarkin Zazzau Jafaru ya fito fili ya nuna cewa zai fi kyau Musulmin lardunan Arewa su riqa kai qararrakinsu ga kotunan Alqalai, amma 'yan lardin jihohin Gabas da Yammasu ci gaba da kai qara ga *Mixed Court*. Shugaban wannan kotun ya san da wannan buri na Sarkin Zazzau.

Saboda irin wannan hali da kotun ta shiga na yawan koke-koken jama'a akan ayyukan Mixed Court ta Sabon Garin Zariya, sai Shugaban kotun a shekarar 1946 ya nemi masarautar Zazzau da ta ba da babban bayaninta akan wannan al amari. Ko da yake an ba da bayanin cewa akasarin koken-keken jama'a ba su da tushe. Amma duk da haka Sarkin Zazzau ya ba da shawara qwaqqwara akan Mixed Court da ayyukanta.

Duk da haka da *qorafe-qorafe*n jama'a suka yi yawa a shekarar 1949, sai Fadar Zazzau ta ba da shawara ta yadda za a qara samun nasara wajen tafiyar da sha'anin wannan kotu. Ga shawarwari da Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru ya bayar, inda ya ce:

Maganar Mixed Court ko da aka yi shawara da mu kafata an nuna za a riqa hukumta mutanen Kudu da al'adarsu ne. Yadda al'ada kan bambanta kuwa wuri uku ne: (a) aure (b) Gado (c) Jayayyar 'ya'ya, sauran laifuka kamar sata, faxa da ba shi, waxannan duk xaya ne. Yanzu da aka kafa Mixed Court sai mu ka ga ana abubuwa da yawa, waxanda suke ba su ne nufinmu da Mixed Court ba. Suna hukumta Musulmi ba da sanin shari'ar Muhammadiyya ba, ko dokokin da muka ba su, su kuwa ba su san Muhammadiyya ba, suna hukumta mutane da dabara ne. Wannan a ganin mu ba dai-dai ba ne, mutanen qasar nan, ba dai-dai muga ana zaluntarsu muna qyalewa ba.

Abin da muka gani, in dai ba tilas ba ne sai a rufe Mixed Courts. A mayar da hukunci baqin da ke qasar nan da mutanen qasar nan a hannun Alqali da su hukunta su da Muhammadiyya ko dokoki. Doka kuwa ba ta rage baqo da xan gari ba. Idan wani abu ya tashi na al'ada sai a nemi masanan al'ada. Na duba a cikin shekara ba su da sakar aure ko gado ko jayayyar xa. Ganin haka shi ya sa muka ce a mayar da shari'arsu ga alqalai don hukuncin qasa ya zama dai-dai. Su kuma mutanen Kudu su daina mana girman kai kamar ba su na qarqashinmu ba. Dukkan baqon da ke qasar nan yafi kyau a hukunta shi da shari'ar mutanen qasar nan. Idan al'adar shi ta samu, su Alqalai su tambayi masanan al'adarsu su ba da fatawa. Su Alqalai su yanke hukunci da fatawar da suka bayar kamar yadda muka anbata sama. In kuwa ya zama tilas ne sai mu haqura domin mun ga Jos mutanen Kudu can sun fi na Kaduna da Sabon Garin Zariya yawa amma babu Mixed Court a can!

M. Jafaru, Sarkin Zazzau,
Zaria, 1/6/1949.

Sufuri da Kasuwanci

Tun cikin shekarar 1911, Turawan Kamfani suka buxe shagunan kasuwanci a Kaduna Jamsin da ke tashar jirgi wato Maqera da Kakuri saboda samuwar zirga-zirgar jirgin qasa. Suna sayen Fatu, da Gyaxa da qoqon qwara da Auduga.

Kasuwancin saye da sayarwa kuwa sai da gari ya kafu sannan aka fara shi, don kasuwar Kaduna, cikin qarshen shekarar 1919, akwai runfuna daven siminti rufin kwano guda huxu, da rumfunonin ciyawa da zana kuma goma sha-uku. Su waxannan davavvun runfunan, an yi su ne don mahauta su samu damar tsabtace kwatar su da kyau. Sauran rumfunoni kuwa na 'yan dako da masu sayar da kayayyakin masarufi ne.

Wajen 'yan awon hatsi kuwa, wani lokaci farashin kuxin mudun awo yana hawa, ne a duk lokacin da kuxin jirgi ya qaru. Dalili kuwa mutanen garin Kaduna

a manoma bane don, galibinsu leburori ne ko ma'aikatan gwamnati. Don haka suka dogara ga manoman waxansu garuruwa kamar Minna da Zariya ko Kano, wajen samun abinci waxanda suke aikin noma a garin qalilan suke. Ko da yake an yi qoqari an kawo mudun awon da ya dace, amma duk da haka a duk lokacin da aka yi qoqarin qayyade farashin kayayyaki don hani ga cin qazamar riba, sai kasuwar ta fashe, 'yan awon watsewa suke yi. Don haka tilas aka barsu suka riqa sayarwa yadda suke so. Kowane xan kasuwa mai rumfa yana biya mata kuxi a kowace rana wato kuxin rumfa kwabo xaya.

A hankali sai kasuwar ke cika saboda havakar jama'a. Domin tsabtar kasuwa da karvar kuxaxen runfuna, sai aka naxa Sarkin Kasuwa, wanda aka kuma danqa masa nauyin kula da kasuwar da karvar kuxin runfuna. Sarkin Kasuwar farko a wannan gari shi ne wani tsohon soja mai suna Mai Damusa. Daga shi ne sai sarautar kasuwa ta zo kan Garba Tasawa (Samanja). Daga baya Malam Bala da Malam Barau Mai Tatsuniya suka yi sarautar kasuwar Kaduna.[1]

Kasuwar Kaduna a shekarar 1920 ta qara girma tana da manyan runfuna masu rufin kwano da daven simiti guda huxu, da runfunan zana da rufin tabarma guda goma sha-uku. A wannan kasuwa ana sayar da da hatsi da sauran kayayyakin masarufi, mahauta kuma na sayar da nama.[2] A hankali sai kasuwar ta shiga havaka cikin hanzari. Saboda bunqasar jama'a da ake samu a kullum, sai tattalin arziqin jama'ar gari ya shiga qaruwa a hankali. Mista C.M Brown shugaban Kaduna *Township* wato *Station Magestrate* ya ba da labarin qarin bunqasar tattalin arziqi a cikin shekaru shida daga shekarar 1923 zuwa 1929.[3]

An sami qaruwar kuxin shiga wato *Internal Revenue* wanda hukumar Kaduna *Township* ke samu daga kuxaxen haraji daban-daban. A shekarar 1922 aka fara samun qaruwar arziqi sosai. Mista C.M Brown ya ba da kasafin qarin kuxin shiga kamar haka: fam xari da takwas da sulai huxu (£108.4) daga harajin kasuwa, da fam xari uku da hamsin da tara da sulai tara da sisi (£359.9.6d) daga harajin mahauta. An kuma sami fam maitan (£200) daga harajin jama'ar gari.[4] Wato an samu jimilar kuxin shiga da ya kai fam xari biyar da talatin da uku (£532) a qarshen shekarar 1926/27; fam xari uku da casa'in da biyu (£392) a qarshen shekarar 1927/28; da fam xari tara da saba'in da xaya (£971) a qarshen shekarar 1928/29.[5]

---

1 Hira da Malam Tanimu Zariya, a Kaduna ran 25 ga Mayu 1984.

2 NAK, SNP, 141/1821

3 *Ibid*., Zarprof 2572

4 *Ibid*., 9, 76/1923; *Kaduna Township Annual Report* for 1929

5 *Ibid*., 172 11617

Ko da yake Kaduna cibiyar mulki ce da rundunar sojoji, amma duk da haka ana samun bunqasar sufuri da kasuwanci, hukuma kuma na samun qaruwar kuxin shiga. A shekarar 1929 kashi uku bisa huxun 'yan kasuwan wannan gari sun dogara ga ma'aikata da sojoji ne wajen sayar da kayayyaki. An kuma samu 'yan kasuwa da suka yi suna a Kaduna *Township* da sauran garuruwan Arewa.

Akwai wata Bakanuwa hanshaqiyar attajira 'yar kasuwa, mai suna Kashi-Kano wadda ta shahara a garin Kaduna. Ita Badunguriya ce ta na kuma cikin manyan attajiran gari da suka fara mallakar mota a Kaduna. A shekarar 1924, ne Kashi Kano ta sayi motar safa samfurin *Reo Lorry* domin ta qara bunqasa sana'arta ta sayar da hatsi da kayayyakin abinci. Tana kuma amfani da wannan motar wajen xaukar kayayyakin abinci a duk sassan gari da ke Arewacin kogin Kaduna.[1]

A shekarar 1926 sai ta nemi iznin shiga da kayayyakin abinci zuwa qetaren kogin zuwa Maqera domin bunqasa kasuwancinta. A kwai leburori da fasinjoji da ma'aikata masu yawa a wannan waje. Yawan mutane kuwa ai shi ne kasuwa. Saboda haka sai wannan attajira ta nemi ta riqa zuwa cin wannan kasuwa. Amma abin takaici, sai hukumar Kaduna *Township* ta qi ba ta izni. Saboda haka sai ta kai hukumar qara ga Razdan na Zariya, domin ya duba kukanta da idon rahama ya taimaka a bata iznin kai kayayyakin abinci zuwa kudancin kogin Kaduna.[2] Wato dai tana son ta buxe shagunanta a Kaduna Jamsin.

Kashi-Kano hanshaqiyar attajira cewadda ta yi suna wajen taimako da karimci a garin Kaduna. Ita wannan Kallabi Tsakanin Rauwuna ta yi qoqari gaya wajen tallafawa mata domin su bunqasa sana'oinsu. Abin da ya kamata halayyarta ta baiwa Turawan mulki sha'awa. Amma abin takaici sai aka hanata iznin zuwa Maqera don kasuwanci, duk da cewa tana xaya daga cikin manyan attajiran gari da ke biyan haraji.

Hukumar Kaduna *Township* ta yi suna wajen matsawa leburori da 'yan tireda, da sauran 'yan kasuwa wajen karvar haraji da kafa masu tsauraran matakai iri-iri. Alal misali, Ahmadu xan tireda ya sawo buhunan dawa ashirin da uku da rabi daga garin Gwagwada da ke yankin Neja. An sauke masa waxannan buhunan hatsi a tashar jirgi ta Kaduna Jamsin, amma saboda ance bai yi hanzarin kwashesu ba, sai da aka ci shi tarar kuxi har fam huxu da sulai goma sha-biyar (£4.15.0d). Wato wajen neman qiba ya samo rama. Domin kuwa a maimakon ya sami riba sai wannan haraji ya sa shi yin mummunar asara. Saboda haka shi ma bai yi watawata ba sai ya kai qara ga Razdan na Zariya.

Duk da cewa a wannan lokaci ana wuyar abinci a garin Kaduna, amma abin mamaki shi ne yadda hukuma ke xora harajin sulai biyu ga kowane kayan da aka sauke a tashar jirgi da kai wa kasuwa. Idan kuma kayan da aka sauke ya daxe ba a

---

1 NAK, SNP, Zarrof K. 1130 Vol. 1 2611/24; *Zaria Province*: Complaint

2 *Ibid*., K 1130 Vol. 1

kwashe ba, za a qara biyan kuxin harajin wannan wuri wato *demurrage*. Dalilin haka ya sa hada hadar kasuwanci wajen amfani da hanyar jirgi ta shigo da kayayyakin abinci ya zama babbar matsala ga 'yan kasuwa. Wannan ba qaramar matsala ba ce musamman idan aka yi la'akari da biyan harajin sulai biyu akan kowane kayan da'aka xauko daga tashar jirgi zuwa kasuwa. Biyan wannan kuxi da *Station Magestrate* ya sanya, wa 'yan kasuwa ya sa jama'a sun bijirewa wannan doka. Duk da matsalolinda 'yan kasuwa suka fuskanta a wannan gari, an sami ci gaba sosai da samun qarin jama'a da sauye-sauyen shugabannin gwamnati da na hukumomi tare da buxe shaguna da kantuna a wannan gari.

A shekarar 1922 aka fara samun kafa kantuna a sabon garin Kaduna. An kafa kantuna guda uku. Kantuna guda biyu; na Turawan Kamfani ne da ake kira *Niger Company* da na *Messers Man Pole and Company*. An kafa su ne akan *Lagos Street* da *Market Road*. Xaya kantin *Messers Miller Brothers* a unguwar Turawa aka kafa shi.[1] An samu qarin bunqasar sufuri da kasuwanci da aka kafa waxannan kantuna saboda suna shigo da kayayyakin masaqa da sabulai da kayayyakin girki da na'alatu iri-iri. Saboda haka sai aka samu qarin 'yan tireda da diloli a garin Kaduna. A hankali kuma sai garin yana zama wata babbar cibiyar kasuwanci a Arewa. Daga samun qarin kantuna sai aka samu karin shaguna da manyan kantuna da masana'antu.

Ko da yake Kaduna, gari ne na ma'aikata amma da aka samu bunqasar masana'antu sai garin ya samu bunqasar kasuwanci cikin hanzari.Sufuri da kasuwanci sun bunqasa sosai saboda kwararowar 'yan da 'yan tireda da aka samu da kafuwar masana'antu. sana'a ce da ta kafu sosai a wannan garin. Karuwar saye da sayarwa a shaguna, da masu talla a titi sun taimaka wajen bunqasar kasuwanci. Hanyar jirgi da hanyoyin mota da suka haxa garin da qauyuka da birane a Nijeriya, sun taimaka wajen shigo da kayayyaki iri-iri musamman daga qetare. Haka kuma kayayyakin da aka sarrafa daga masaqun Kaduna na samun kasuwa a garuruwa masu yawa a Nijeriya da *qasashen* qetare.

Farashin kayayyakin masarufi kan sami hauhawa saboda dillalai da ke tsauwala farashin kayayyakin kafin su kai ga mai saye. Dalilin haka ya sanya manyan kamfanoni amfani da diloli wajen sayar da kayayyakin da suka sarrafa. Saboda yawan masan'antu sai aka samu diloli iri-iri da ke hurxa da waxannan masaqu da kamfanoni. Domin haka sai sana'ar da dillanci suka bunqasa sosai a garin Kaduna.

An samu qaruwar kamfanonin sufuri da ke shigo da kayayyakin qetare a garin Kaduna. Da yawa waxannan kamfanoni, sun maida Kaduna ne cibiyar kasuwancinsu a Nijeriya. Waxansunsu kuma sun buxe rassansu a wannan gari.

---

[1] NAK, ZarProf, K 1130 Vol. 1

Manyan kamfanonin sun buxe manyan shaguna da suke sayar da kayayyaki iri-iri. A yankin da waxannan shaguna da runfuna suka fi yawa, ne ake samun jama'a masu yawa wajen saye da sayarwa, saboda haka sai wannan waje ya zama shi ne cibiyar kasuwancin wannan gari wato *Central Business District* (CBD).

A Kaduna cibiyar saye da sayarwa, an yi mata tsarin da ke bambanta shagunan Turawa da Indiyawa da Qwarori daga 'yan qasa, saboda bambancin tsarin mahalli da bambanci unguwanni da aka kafa tun farko. Tudun-Wada sai ta zama mazaunan 'yan kasuwa da masu sana'a. Saboda haka sai wannan unguwa ke kusa da babbar kasuwar Kaduna domin samun sauqin bunqasa sana'arsu. 'yan kasuwa kuma ba za su sha wahalar zuwa kasuwa ba. A wancan lokaci da yawa kan tako saiyadarsu daga gidajensu ne zuwa kasuwa ba tare da wata wahala ba.

Ko da yake babu wani waje da aka kafa don ya zama cibiyar kasuwanci amma babban titin *Prince Edward* (Ahmadu Bello Way) shie ne ya zama kamar cibiyar kasuwancin wannan gari. Akwai manyan kamfanoni da shaguna a kan wannan layi, waxanda ke sayar da kayayyaki iri-iri musamman waxanda aka kawo daga qetare. Waxannan shaguna da kamfanoni na Turawa da Qwarori ne. Akwai kamfanoni kamar *Unted African Company* (UAC), da *A.G Leventis and Co. (Nig) Ltd*., da *Bewac Ltd*., da *John Holt Ltd*., da *K. Chellaram and Sons (Nig.) Ltd*., da *Union Trading Company Ltd (UTC)*.[1] Duk waxannan manyan kamfanoni sun faro ne daga matsayin wuraren ajiyar kayayyaki wato *warehouses*. Daga nan sai suka buxe shaguna da kantuna da manyan kantuna (super markets) don bunqasa saye da sayarwa.

Kasuwanci na da alaqa da tsarin Kaduna na tun fil azal. Mazauna Sabon Garin Doka suna zuwa kasuwanni irin na saye da sayar da kayayyakin masarufi da kayayyakin gargajiya. Haka kuma mazauna Unguwar Turawa sun fi zuwa shaguna da kantuna da manyan kantuna wajen sayen ababen masarufi da na more rayuwa. Sana'ar ta 'yan qasa ce saboda kafin shekarar 1974 manyan kamfanoni da shaguna na hannun baqi ne musamman Turawa da qwararo da Indiyawa.

A shekarar 1974 ne gwamnati ta kafa dokar maida kamfanonin baqi ga 'yan qasa ko *Indigenization decree of 1974* wadda ta baiwa 'yan qasa ikon mallakar waxannan kamfanoni, kamar kamfanin *UAC* da *UTC* da *Bewac* da Hashim *Store*, da *Chellarams* da *John Holt* da *Mandilas*.[2]

Ko da yake an kafa Kaduna ne saboda ta zama cibiyar Mulkin Mallaka, amma sai garin ya zama qasaitaccen cibiyar kasuwanci wadda ta taimaka wajen bunqasar kasuwanci da masana'antu a Arewa musamman a lokacin da garin ya

---

1 *Max Lock, Kaduna*, shafi na 148

2 *AK Medugbon, Kaduna* shafi na 250

zama yankin Hedkwatar Arewa ko *Capital Territory* a shekarar 1956.[1] A yau Kaduna ce ta biyu a bunqasar kasuwanci, bayan Kano, kuma garin na cikin manyan garuruwa da ke da bunqasar masana'antu. Ko da yake yawancin waxannan masana'antu sun durqushe saboda tavarvArewar tattalin arziqin qasa, amma duk da haka an samu Gwamnatocin soja da na Farar hula da suka yi qoqarin tayar da da waxannan kamfanoni da masana'antu.

Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato ya taimaka gaya wajen maida Kaduna babbar cibiyar kasuwanci da masana'antu a Arewa. Kaduna na da albarkar masana'antu. An kafa Masaqar Kaduna, *Kaduna Textiles Ltd*. A shekarar 1957. Wannan babbar masaqa tana samarwa xaruruwan ma'aikata sana'oi daban-daban. Haka kuma dubban 'yan kasuwa sun yi arziqi ta hanyarta. Bayan shekara goma da kafata wato a shekarar 1965 ta na da ma'aikata da suka yi kusan dubu bakwai (7,000). An kuma sami qarin masana'antu kamar Masaqar Arewa da *Norspin* da Masaqar *Northern Nigeria* da Masaqar *United Nigeria*. Saboda haka sai garin ya samu manyan masaqu guda biyar.

A watan Oktoba na shekarar 1963 Ma'aikatar Ciniki da Masan'antu wato Trade and Industry, ta yi amfani da rohoton *Sir Alexander Gibb and Partners* wajen kintata bunqasar da masana'antu za su yi a nan gaba. A wancan lokaci an hangi samun qarin ma'aikatar yin barasa wato *Brewery* da bunqasar masaqun da ke akwai. Wannan rahoto ya hangi qarin samun kamfanoni kamar: (a) Kamfanin yin fenti wanda zai ta xauki mutane sittin da (b) Kamfanin yin robobi wato plastic factory wanda ake son kafawa a Kaduna ko Kano. Shi wannan kamfani na da qarfin xauqar mutane saba'in da Kamfanin yin fantimoti wato *Suitcase*, wanda ake son a fara kafawa a Kano. Duk waxannan kamfanoni ana son kada su wuce faxin eka goma.[2]

A shekarar 1963 rahoton *Gibb* ya kintata cewa qarfin masaqun Nijeriya ta Arewa zai kai yawan yin yadi mirabbain miliyan xari biyar da sittin (560 million square yards per annum) a shekarar, a 1972.

Mallakar Gida da Fuloti

Ranar 1 ga Janairun shekarar 1920, *Station Magestrate* kuma mataimakin kwamishinan 'yan Sanda, Mista *T. Stone* ya vullo da amfani da takardar shaidar mallakar gida ko fuloti. A qarshen shekarar 1919, akwai fulotai xari biyu da saba'in da tara a cikin sabon gari waxanda aka yi masu rajista. Saboda kada saye ko kyauta da fuloti ya kawo rikici tsakanin jama'a, sai Mista *T. Stone* ya qirqiro da yin amfani da takardar shaidar saye da sayarwa kamar haka:-

---

[1] NAK, ZarProf, K 1130 Vol. 1

[2] *Ibid*.

Ni……. Mai fuloti mai lamba ……..a cikin Kaduna na amince da ya koma ga Mallakar ……. Daga wannan rana …….. Sa hannun mai sayarwa …….. Shi kuma mai Saye: sai ya cika kamar haka: Ni……Na yarda da karvar fulotin daga hannun…….. mai lamba ……. A waje ……. cikin Kaduna 'Township', a qarqashin qa'idar da aka rubuta a ofishin "Station Magestrate " daga yau ranar……..na amince da biyan haraji ko kuxin hayar wannan fuloti kamar yadda ake buqata……Kwanan wata.

Sa hannun mai saye

Sa hannu a Kaduna ……ran ……

Sahannun Majistare

(Station Magestrate)

Wannan muhimmin abu da wannan baturen 'yan Sanda ya kawo, ya rage rigima a kan mallakar fulotai. Saboda haka ne cuta ko danniyar fuloti ta zamo abu mai wuya. Saboda in ka yi furucin kai ka mallaki fulotin, to, ina takardar shaidar mallaka wato *Certificate of Occupancy*. Saboda haka kowane gida ko fili yana da wannan takardar shaidar mallaka, har yanzu ana bin wannan tsarin.

Tsabtar Gari da Muhalli

Tsabta muhimmiyar aba ce ga rayuwar xan-Adam, saboda cuce-cuce da varkewar annobar ciwo na da dangantaka da qazantar jiki muhalli da gari baki xaya. Don gudun tsoron varkewar annobar ciwo, sai hukuma ta tilasta wa jama'a da su tsabtace garin Kaduna da Doka, duk wani mai qazanta, to, zai xanxana kuxarsa don kuwa za a hukunta shi da doka mai lamba 3 da 6 da suke cikin rukunin dokokin gari ta shekarar 1917.

Haka kuma cikin waxannan dokokin akwai dokar kula da lafiyar jama'a wadda ta yi hani ga kowane mahaluki da ya yi watsi da shara, kayayyaki ko yin najasa ba bisa qa'ida ba. Duk mai son zubar da shara, ko vawon rake ne, to, dole ne ya zubar cikin 'yan gArewanin shara. Su waxannan wuraren zubar da shara, an sanya masu alamar 'jar tuta don jama'a su lura da su, kuma su riqa zubar da shara a cikinsu. Saboda waxannan matakan da aka xauka abu ne mawuyaci ka ga mutum yana tafiya yana shan rake a hanya, don sai nan da nan a yi wuf da shi a cizgi kuxin tara a jikinsa. Domin hukuma bata wasa da kwasar shara.

Kwasar Shara

Kula da tsabtar gari da mahalli ya samu kyakkyawan tushe a garin Kaduna saboda muhimmacin da Turawa suka ba shi. A lokacin mulkin Turawa har ya zawa mulkin 'yan siyasar farko, garin Kaduna ba shi da na biyu a wajen kula da tsabtar gari da mahalli, a kusan faxin Nijeriya baki xaya. Amma kula da tsabtar gari abu ne da ke da tsada sosai, musamman idan garin ya riqa samun qaruwar jama'a da masana'antu. Kaduna ta taso da tsarin kwasar shara a kowane lungu a

wannan gari. Hukuma ta xauki tsarin tafiyar da kwasar shara cikin hanzari saboda barin tarin bola a layuka zai vata kyawon gari, zai kuma kawo wata barazana ga lafiyar jama'ar gari.

Akwai hanyoyin kwasar shara guda uku: A tanadi wajen zuba shara a rami babba wato *Controlled Tipping*, (ii) qona-shara a wasu xakuna na musamman wato *Incineration* da (iii) qona wasu abubuwa daga shara wato *pulveration*. Duk waxannan hanyoyi ana amfani da su a sassa daban-daban a garin Kaduna domin a tabbatar da garin da mahallin jama'a na cikin tsabta sosai, kuma babu wani wanda ya yi wa dokar da ta hana zubar da shara a ko'ina karen-tsaye. A wannan lokaci garin Kaduna, abin nuna misali ne wajen kyau da tsabta a Nijeriya.

An fi amfani da hanyar zubar da shara a rami babba ko awani babban kwazazzabo da aka tanada. A kowane layi an tanadi wuraren zuba shara daga gidaje bisa qaixa. A wasu layuka kuwa akwai wurare da aka gina na musamman domin zubar da shara ana kiran wannan waje bola, a wasu layuka kuma manyan bokitai aka ajiye a wurare da motar shara ka iya bi ta kwashe su. Kusan kowane layi akwai wajen zubar da sharan sa. Hukumar da ke kula da tsabtar gari da mahalli na da ma'aikata iri-iri a qarqashinta. Tana da jami'an duba tsabtar gida da layi wato Duba Gari. Aikinsa ya bi layi-layi da gida-gida yana ganin yadda gidaje da unguwanni ke kula da tsabtar wurarensu. Akwai mata masu shiga gidan kulle. Hukumar na da ma'aikata da motocin kwashe shara iri-iri.

Motocin kwasar bola da leburorinta na bi layi-layi da lungu-lungu suna kwashe bolar gidaje da unguwanni. Su kan bi unguwanni sau xaya ko sau biyu a mako. A wuraren da jama'a ke da yawa, ma'aikata kan bi waxannan layuka da marecen kowace rana. Saboda haka bokitan shara da bololin kowace unguwa ba a barinsu su cika su batse. Ana kwashe su akai-akai. Haka kuma jama'a ba sa zubar da shara ba a bisa qa'ida ba. Sannan kuma gwamnati ta baiwa wannan aiki mai tsadar tafiyarwa muhimmanci sosai. Dalilin haka ya sa ma'aikata ke samun qarin motocin kwashe-shara da qarin leburori a kowace shekara. Domin hukuma na la'akari da cewa qarin jama'a ke sanya qarin shara.

Idan motocin kwashe-shara suka cika sai su kai wani babban kwazazzabo da ke wajen gari a inda aka gina Scala Cinema a yanzu, su zubar da shara a wannan wajen. Saboda haka sai wannan tsari na zubar da shara da ake kira *Controlled Tipping* ya kawo tashin wata babbar bola a wannan waje da ake kira Bolar Oyoyo. Ita wannan babbar bola ta yi suna sosai a garin Kaduna saboda a wannan bola ce ake zubar da sharar unguwar Turawa. A cikin wannan shara ce mutane ke samun abubuwa masu kyau da amfani, waxanda Turawa suka zubar idan ba sa so, ko kuma suna gaggawar barin garin Kaduna a lokacin da suke hanzarin zuwa kama aiki a wani gari. Ire-iren kayayyakin da ake sayarwa a gwanjo a yanzu, a wancan lokaci zubar da su ake yi a Bolar Oyoyo.

Ita wannan babbar bola tana daga wajen sabon Gari ne saboda ana gudun varkewar gobara idan aka bar ta a cikin gari. A wancan lokaci titin Lagos street shi ne kusan qarshen sabon gari saboda daji ne babba a tsakanin layin Prince Edward da wannan babbar bola sai tsirarun gidaje kawai. Ta hanyar zubar da shara ne aka cike babbar kwazazzabo da fadamar wannan waje. A kan wannan bola ce aka gina gidan sinima wato Scala Cinema da sauran gine-gine da suke wannan waje a yanzu. Wato dai *Controlling Tipping* na taimaka wa wajen cike ramuka da kwazazzabai a cikin sauqi ba tare da an kashe maqudan kuxi wajen xauko qasa ko duwatsu ba. Haka kuma ita wannan hanyar zubar da shara na taimakawa wajen samar da taki wato *Fertilizer*. Saboda a ramin da aka zuba shara ya kan xauki shekaru masu yawa kafin shara ta nuna har ta zama taki wanda manoma ka iya amfani da shi.

Ita kuma hanyar qona bola wato *Incineration* tana da amfani da kuma tsadar tafiyarwa, tana da matsalar hayaki da wari da tartsatsin wuta a inda ake qona bola. Ana amfani da wannan hanya cewajen qona shara a wani rumbu na musamman ne wato incinerator wadda ba ta xauke da kwalebe da qarafe da makamantansu ba. Amma idan aka cire waxannan ababe, ana qona su ta hanyar niqar da su har su zama gari wato pulverisation. Ita wannan hanya tana dandaqe kwalabe da qarafa ne da ke cikin shara kafin ta maida su taki. Amfani da waxannan hanyoyi sun taimaka wajen tabbatar da tsabtar gari da mahalli a Kaduna. Haka kuma an xauki hanyar kwashe najasa bisa tsarin da Turawa suka kawo.

Kwashe Najasa

Kaduna na qaruwa da jama'a cikin hanzari. Saboda haka buqatar samar da ruwan sha, da kwashe shara da najasa sai suka qaru sosai. A duk inda jama'a suka yi amfani da ruwa, wajen harkar rayuwa akan sami qarin najasa da na ruwan lambatu. Saboda haka ya zama tilas a xauki matakan kwashe su a bisa tsari mai kyau a kuma cikin hanzari, a wani tsari da ake kira *System of Sewerage and Sewage Disposal*. Yin haka ya zama tilas domin gudun kada najasa ta gurbata hanyoyin ruwan sha da muhalli, wanda ka iya haifar da varkewar ciwon amai da gudawa musamman ciwon mai baushe. Qarin buqatu da amfani da ruwa ga jama'a da masana'antu, ya kamata ya tafi dai-dai da qarin tsarin kwashe najasa da shara abubuwan da ka iya kawo barazana ga lafiyar jama'a. Haka kuma qarin jama'a ke haifar da qarin shara da kwashe najasa.

Akwai hanyoyi guda huxu da ake amfani da su wajen kwashe najasa waxanda suka haxa da: (i) Masai (Shadda); (ii) Amfani da Masan Bokiti (iii) Amfani da kora najasa da ruwa, da (iv) Amfani da Water Borne System. An yi amfani da duk waxannan hanyoyin a sassa daban-daban a garin Kaduna, a kuma lokuta daban-daban.

A unguwanni kamar Kawo, da Unguwar Shanu, da Abakpa, da Tudun-Wada da Tudun-Nufawa, da Maqera da Kakuri an ce kashi talatin da uku da rabi (33.5%) na jama'ar waxannan wurare suna amfani ne da shadda. Amma a rabin Gabashin Tudun-Nufawa kuwa, jama'ar wannan waje sun fi amfani da masan bokiti.[1] Yankin wannan unguwa na maqabtaka da sabon garin Doka inda ake amfani da masan bokiti sosai.

Yankin Gabashin Tudun-Nufawa da Sabon Gari har a wajejan layin Barno da vangaren kudancin Kaduna, Max Lock ya ce kashi arba'in da biyu da rabi (42.5%) na mazauna waxannan wurare sun fi amfani da masan bokiti, ya qara da cewa:

"Ana kwashe najasar waxannan wurare a bokitai, inda ake zuba su a kwatashin siminti babba, daga nan sai mota ta kwashe, in najasar ta cika kwatashin maqil, sai a kai wani waje na musamman da ke Kudu maso Yammacin gari. A wannan waje ake sarrafa najasar da aka kwaso. Xaukar kashi abu ne mawuyaci saboda yadda wannan hanyar kwasar najasa ke tayar da hankali, da wuya a 'yan shekaru masu zuwa a sami waxanda za su yi wannan qasqantacciyar sana'ar xaukar kashi." [2]

Ko shakka babu sana'ar xaukar kashi, sana'a ce da ta vullo a garin Kaduna. Turawa ne suka kawo ta. A Arewa amfani ake yi da masai a birane da qauyuka. Amma a zuwan Turawa ne sana'ar xaukar kashi ta fito babu kuma inda ake yinta sai a Kaduna.

A wuraren da ma'aikata da shugabanni ke zaune da kuma manyan makarantu, ana amfani da *Septic Tank* wajen yin najasa da kwasarta. Ita wannan hanyana amfani ne da babban rami da ke kusa da bayan gida a kwamin da aka daxe da siminti wanda ake kira wato *Septic Tank* inda ruwan najasa ke kwararowa ta babban bututu har ya taru. Idan wannan kwatashi ya cika maqil da najasa sai mota ta musamman ta zo da na'urori ta janyeshi ta kai inda ake sarrafa shi.

Ita wannan hanya tana da tsabta sosai saboda kowane gida na da nashi masai ko *Septic Tank* wanda aka gina na musamman. Kuma duk xakunan bayan gida, a wannan babban tanki najasarsa ke kwararowa. An ce kashi tara bisa xari (9%) na jama'ar waxannan wurare, ne ke amfani da wannan hanya. Ko shakka babu wannan tsari ya fi na shadda da masan bokiti tsabta sosai, amma tsarin da yafi wannan kyau da tsabta kuwa shi ne na *Water-borne System*.

Ita hanyar kwasar najasa ta water-borne system, ana amfani da ita ne a wasu wuraren sojoji da makarantun horar dasu, da Asibitoci da manyan otal kamar Hamdala Otel. Ita najasar takan bi wurare da aka tanada wajen sarrafata kafin abi

---

[1] Maxlock, *Kaduna*, shafi na 116

[2] *Ibid*.

da ita ta babban bututun da za ta kwaranye ta bi kogi ko wani babban rafi. Ance kashi goma sha-biyar bisa xari (15%) na wurare manya, ne ke amfani da wannan hanya.[1]

Sana'ar Xaukar Kashi

Sabon Garin Doka ya havaka qwarai, jama'a kowa ya samu muhallinsa. Ana nan sai Turawa suka sa wasu jama'ar garin kwasar kashin gidajensu daga Unguwar Turawa, suna tafiya bayan gari (Kabala) suna zubarwa. Irin wannan aikin kashi da ya faro daga unguwar Turawa, sai a hankali ya shigo cikin Sabon Garin Doka. Da farko dai masan bokiti (Bucket Latrine) sai a Unguwar Turawa ake amfani da shi, don su mazauna Sabon Gari, salga suke haqawa a gidajensu.

A hankali sai ya zama gidaje da yawa suna amfani da shi maimakon salga. Ma'aikatan xaukar kashi sai su riqa bin bayan layi suna kwashe kashin kowane gida, suna tafiya can Kabalar Kashi suna zubarwa. Su waxannan masu sana'ar ana kiran su "Tula " (Bade-bade). Idan lokacin aikinsu ya yi sai su yi shigar vadda kama, su xauki bokiti a kawunansu sannan su riqe tsintsiya a hannayensu. Aikinsu bin layi-layi suna duba bokitin kashin kowane gida, duk bokitin da ya cika sai su jirkice a bokitansu, su kuma sa tsintsiyarsu su katse bokitin sosai kaf in sun xauka sai su nufi bayan-gari. A lokacin da suka xauko kashin sai qudaje su riqa binsu buu! Kamar xangon zuma.

A can bayan-gari kuwa, an tanadi wajen zubar da kashin a wani irin kwatashi-kwatashi wanda aka dave da siminti. In duk kwatasan sun cika maqil da kashi, to, sai motar kwashe kashi ta zo ta janye kashin ta tafi da shi inda za a sarrafa shi don amfanin manoma wajen yin taki.

Sana'ar xaukar kashi, sana'a ce mai albashi tsababa, amma ba ta da farin jini ko kaxan. Ba kowane mutum ne zai daure yin irin wannan sana'a ba, saboda qyamar tsoron xaukar cuta iri-iri da kuma ba ta dace da addininmu ba. Domin musulunci Addini ne mai buqatar tsabta sosai, babu tsabta ga wanda yake wannan sana'ar.

Saboda haka su masu wannan sana'a ba sa so a san suna yin wannan aiki, don haka ne masuke shigar vadda kama. Lokacin aikinsu, galibinsu suna aiki da daddare ne, ko kuma asubahin fari, kafin safiya sun gama aikin wannan rana. Amma waxansun su kuwa da rana suke aikinsu, ido-na-ganin-ido don ba abin da ya dame su.

Ita wannan mummunar sana'ar xaukar kashi, wadda kafuwarta sai da aka yi tajin-tajin, saboda jama'a ba su qaunarta kuma tilasta su aka yi da har ma aka kusa a ce a kowane gida a daina amfani da salga sai bokiti, amma shirin yaci tura. Daga qarshe, Qaramar Hukumar Kaduna lokacin Alhaji Yusufu Xantsoho ta kashe

[1] Maxlock, *Kaduna*, shafi na 116

wannan sana'a. Shi ya sa yanzu ba ka ganin masu wannan aiki. Da sun ratsa hanyar da jama'a ke zaune, sai duk wajen ya gume da wari, qudaje na bin su xuu! xuu!! Yara kan takalesu, su kan yi masu ihu suna kiransu tula! bade-bade!! mai xaukar kashi!!! Wani lokaci kuma sai an tsawatar masu!

Idan tula ya gama aikinsa na kwasar kashi, sai ya yi wanka a rafi ko kuma a wani gulbi a bayan-gari, sannan sai ya shiga kayayyaki masu kyau ya shafa turare mai xan karan qamshi, kafin ya shigo gari aljihu cike da sulalla. Yana tafiya yana qwambo, in ba ka san shi da wannan sana'ar ba, sai ka yi masa kallon wani babban attajiri. Da yawa daga cikinsu matansu ba su gane, cewa suna sana'ar xaukar kashi sai ranar da rana-ta-vaci sannan in asirinsu ya tonu matan nasu su gane.

Samar da Ruwan Sha

Ruwa muhimmin abu ne ga rayuwar xan-Adam. Rayuwar xan-Adam ta dogara ga ruwan sha, da abinci da iska. Duk inda 'yan-Adam suka taru, xaya daga cikin manyan abubuwan da za su yi shi ne, tanadar wa kansu ruwan sha. Allah Ya albarkaci Kaduna da isasshen ruwan sama da tafkeken kogi. Isasshen ruwan sha yana xaya daga cikin dalilan da ya sa aka kafa wannan gari. Buqatar ruwan sha da na aikace-aikace yana da dangantaka da yawan jama'ar alqarya.

Yawan jama'ar wannan gari da ke zaune a Kaduna a cikin shekarar 1917 sun kusa yawan mutane dubu biyar (5,000), kuma suna havaka cikin hanzari. Wannan dalili ya sa ma'aikatar ruwa da ke qarqashin Firdaburdi ta duqufa wajen ganin waxannan jama'a sun sami isasshen ruwan sha da na aikace-aikacen yau da kullum. Abin da ya tauye wannan babban qudurin wannan ma'aikata, shi ne rashin isassun kayayyakin aiki, don haka an jima ana xan qarancin ruwan sha a Kaduna, amma rijiyoyin da aka gina a wannan lokaci sun taimaka matuqa.

Kafin famfunan ruwa su kama aiki sosai an rubuta wasiqu masu dama tsakanin Daraktan Fidaburdi da Sakataren Lardun Arewa. Ga wasu misalai:

Sakatare,

An yi shirin sanya famfo guda xaya a Unguwar Akawuna; guda xaya a Barikin Soja da kuma guda biyu a Sabon Garin Doka. Amma ba za a fara amfani da su ba, sai an fara aiki da sabon tsari nan da Sati shida masu zuwa, amma banda famfo na Bariki, wanda in ka amince zai fara aiki nan da kwanaki goma. Wata qila, in mun samu saduwa da Mai martaba ko da na minti biyu za mu tattauna akan wannan batu.

Daraktan Fidaburdi Na Lardin Arewa
2.6.17

A kan wannan maganar ruwa, da ke matuqar damun jama'a sai da Daraktan Fidaburdi ya sadu da Gwamna don su tattauna matsolin da aka fuskanta. Haka kuma ya sake rubuta wata wasiqa.

Sakatare,

An lura. Wasiqarka da ta shafi Injiniyan ruwa, ina tsammani maganar famfuna da bututun ruwa an amincewa shirin.

Lurar Mai martaba. Yawan mutane 5,000, da aka bayar a tsanaki, sun fi yawan mutane da ke amfani da su.

Daraktan Fidaburdi
26.6.12

Har-ila-yau, sai da Daraktan ya sake rubuto wannan wasiqa:
Ina da ya bayyan cewa:

Sakatare,

A. Famfunan da ke akwai suna ba da ruwa gallon 3,900 a kullum, suna aiki da safe daga qarfe 6 am na safe zuwa qarfe goma sha-biyu na rana (12 noon); daga qarfe shida na Yamma (6 pm) zuwa qarfe goma sha-biyun dare (12 midnight). A na cika tankunansu sau biyu. Amma duk da injin mai turo ruwa yana aikin awoyi goma sha-biyu (12 hours) a rana, ruwan bai isa.

   A halin yanzu idan wannan inji ya lalace, samar da ruwa zai tsaya gaba xaya; za a kuma xauki lokaci wajen gyaransa. Yana da qarfin xaukar galan 19,000, wanda nan da zai qare, idan injin ya lalace.

B. Matsalar injin da sauransu. Idan aka qaro wani injin, za a samu sauqi sosai. Don za a riqa amfani da shi, a sauran awoyi goma sha-biyu.

   Saboda haka za a nemi qarin ma'aikata da kuxaxe wajen aiki da injina biyu.

C. Injin xin da ake amfani da shi yanzu wato 'Cameroun Pump', kuxinsa wajen £640 ne. In ana buqatar qiyasin *Estimate* wata kuqin wannan sabon injin. Na ba da shawara a rubutawa Daraktan Fidaburdi wannan bayani.

B. Sauthgate
Muqaddashin Daraktan Fidaburdi
9.3.22

Saboda domin a samar da isasshen ruwa ga mutanen Kaduna sai ya zama wajibi a samar da injin xin tura ruwa mai qarfi da qarko. Saboda haka ne Sakataren Lardunan Arewa *Mr. G. S. Browne* bai vata lokaci ba ya aikawa Daraktan Fidaburdi wannan umanni: "Za a sa sabon Fampo ran 31 ga watan Maris xin shekarar 1924. "

An kafa famfo guda xaya a Doka inda ma'aikata da iyalansu ke xibar ruwa. Da safe tun kafin a buxe wannan famfo sai ka ga jerin bokitai waxanda zai yi kusan nisan kwatan mil guda. Saboda jama'a su samu ruwa su kan yi sammako sosai abin da ke haddasa cinKwason jama'a. Saboda haka waxanda ba su sami damar xibar ruwan ba saboda sun yi latti sai su tafi kogin Kaduna su xebo ruwa.

A kwai famfo xaya a sabon Gari a mahaxar layin Kano da layin Ibadan. Akwai kuma guda xaya a Unguwar Akawuna ko *Clerks' Quarters*. An kafa famfo guda a mahaxar titin 'Accra' da layin *King George's Way*. Duk waxannan famfunan ana kulle su da makullai ne saboda akwai lokacin buxe su da rufe su bisa qa'ida. Don kuwa kowane famfo da masu gadinsa, waxanda za su tabbatar da bin doka da qa'ida wajen xiban ruwa.

A cikin watan Yuni na shekarar 1917, sai ma'aikatar ruwa ta rugungun ta kafa famfuna a wurare daban-daban a cikin wannan gari. Alal misali, akwai famfo xaya a kwatas xin akawuna (Clerk Quarters), da xaya a Barikin soja da kuma guda biyu a cikin Sabon Garin Doka.

Dalilin da ya sa ake samun cikas wajen bayar da ruwan sha kuwa, shi ne injin mai janyo ruwa daga kogi ko *Cameron Pump*, ba shi da qarfi sosai. Domin shi wannan *Cameron Pump* yana janyo ruwa mai yawan gallon dubu talatin da tara ne (39,000) a kowace rana kawai, kuma ya kan yi aiki a lokuta biyu ne, kamar yadda Daraktan Fidaburdi ya shirya, wato idan an kunna shi daga qarfe 6am na safe sai ya yi ta aiki har zuwa qarfe goma sha-biyu 12 (noon) na rana, sai kuma a kashe shi ba za a kunna shi ba sai qarfe (6.00 pm) na Yamma inda zai yi aiki har ya zuwa qarfe goma sha-biyu na dare.

Shi wannan injin guda xaya ne tak, idan ya lalace babu maganar samun ruwan sha sai an gyara shi. Duk lokacin da ya lalace sai a ci gaba da yin amfani da rijiyoyi. Ban da haka ma babban tankin ajiyar ruwa wanda ake da shi a wannan lokaci xan qarami ne mai xaukar ruwa kimanin galan dubu goma sha-tara (19,000) kawai.[1]

Ma'aikatar ruwa ta yi qoqarin qaro wani injin amma saboda rashin samun isassun kuxi, wannan abu bai yiwu ba, sai a ranar 31 ga watan Maris na shekarar 1924. Kuxin irin wannan injin kuwa, wato *Cameron Pump*, fam xari shida da *arba'in* (£640) ne. Ruwan sha da lantarki sun samu sosai a garin Kaduna kafin shekarar 1928.

---

[1] NAK/522/1971 *Kaduna Township Water Sushafi na ly*.

Qaruwar jama'a da masana'antu cikin hanzari sun tilasta qarin samar da ruwan sha ga jama'a da na masana'antu a garin Kaduna. Dalilin haka ne ya sa Ma'aikatar Ayyuka, wato *Ministry of Works*, ta ba wani Kamfani mai suna Scott and Wilson Kirkpatrick and Partners, alhakkin dubo hanyoyin da hukumar za ta bi don ta bunqasa samar da ruwa isasshe a Kaduna. Waxannan masana sun yi bincike har sun ba da rahotonsu ga gwamnati a watan Afrilu na shekarar 1966. A wannan rahoto sun ba da shawarwari da a xauki matakan bunqasa qarin samar da ruwa da zai wuce galan miliyan arba'in a kowace rana wato 40m.g.d.[1] A shekaru arba'in da suka wuce Kaduna na buqatar ruwa galan miliyan arba'in a kowace rana. A yanzu sai ayi maganar biliyoyin galan a kullum.

Kogin Kaduna shi ne babban jigon bayar da ruwan sha da na ma'aikatu. Matsalar samar da ruwan sha, matsalace babba tun daga zamanin Turawan Mulki har ya zuwa wannan lokaci. Amma dogaro ga kogi wajen samar da ruwa na da tasa matsalar, saboda koguna a Afirka kan kawo a lokacin damina sannan su janye a lokacin rani. Dalilin haka ya sa aka fi samun ruwa ne da damina amma duk da haka wannan kogi ya taimaka sosai wajen bayar da ruwa a garin Kaduna. Ana kuma samun qarin buqatun samar da ruwa a kowace shekara. Alal misali, domin a shekarar 1965, ana buqatar galan fiye da miliyan huxu a rana (14.12m.g.d), da wajen galan miliyan guda a rana (1.0m.g.d), ga ma'akatun da ke kudancin kogi Kaduna.

Harilayau, kaxawar kogi na da muhimmacin wajen samar da ruwa. Kogin Kaduna kuma kan cika da damina ya janye da rani. Dalilin haka ya sa gwamnati ta buqaci wani Kamfanin Binciken Aikin Ruwa wato *Wallingford Hydraulics Research Station* da ta binciki qarfin kaxawar wannan kogi. A watan Oktoban shekarar 1962 waxannan masana suka yi nuni da cewa ana samun kaxawar kogin mafi qaranci da rani wanda bai gaza galan miliyan shida da rabi da yan kai a rana ba, wato 6.625m.g.d.

Ita ma Ma'aikatar Ayyuka da ke sashen kula da ruwa, wato *Hydrological Section* tun a shekarar 1947 ta sanya ma'aunin da ke gwada qarfin kaxawar ruwan wannan kogi, an kuma qiyasce kaxawar ruwan kogin wato *River Flow* ba ya kasa galan miliyan tara a rana (9.0m.g.d). A watan Maris na shekarar 1959 aka samu kaxawar kogin mafi qaranci da ya kai galan miliyan goma sha-uku da 'yan kai (13.1m.g.d). A rohotonsu Scott and Wilson Kirkpatrick and Partners sun ba da shawarwari da a yi madatsin ruwa babba, a wajen makarantar *Capital School* da ke Malali. Suka ce yin haka zai qara bunqasa samar da ruwan da ba a sarrafa shi ba, wanda zai kai ga yawan galan miliyan ashirin da uku a rana (23m.g.d). Ana iya qara bunqasa shi har ya kai galan miliyan arba'in a rana.[2]

---

[1] MaxLock, *Kaduna*, shafi na 113

[2] *Ibid.*

Kaduna na samun matsalar samar da ruwan sha tun daga wancan lokaci har yanzu. Saboda qarin jama'ar da garin ke samu a kullum wanda, baya tafiya dai-dai da qarin ma'akatar ruwa da kayayyakin aiki. Ana kuma qara himmatuwa wajen bunqasa ma'aikatar ruwa da ke Kaduna ta *Arewa North Treatment-Works*. A wancan lokaci ana tunanin barin irin wannan ma'aikata da ke kudancin Kaduna, wato *South Treatment-Works*, xungurungun.[1]

Samar da Wutar Lantarki

Wutar lantarki na da amfani, wajen sauqaqa rayuwar jama'a da kuma bunqasar da kamfanoni da masana'antu. An bunqasa hanyar samar da wutar lantarki a garin Kaduna musamman a shekarar 1950. A wannan shekarar ce aka kafa Hukumar Samar da Lantarki a Nijeriya wato *Electricity Corporation of Nigeria* (ECN) domin ta xauki nauyin ingantawa da bunqasa samar da wutar lantarki a kowane sashe na wannan qasa. Ita wannan Hukuma ta qara inganta hanyoyin xaukar lantarki da ke da qarfin 132Kv da 330Kv, waxanda ke qarfin baiwa garuruwa lantarki da ke da nisan xaruruwan mil tsakaninsu. Tunda an fahimci buqatar samar da wutar lantarki za ta qaru a wannan qasa a cikin shekaru masu zuwa, sai aka yi binciken yadda za a yi amfani da qarfin zuwan kogin Kwara wato *Hydro-Electric Potential*, wajen samar da wutar lantarki a shekarar 1958. A wannan qasaitaccen shiri, aka kafa Hukumar Madatsar Ruwan kogin Kwara wato *Niger Dams Authority*, a shekarar 1963. A matakin farko na wannan shiri kuwa madatsar ruwan da ke Kainji da Jebba da Shiroro, za su ba da wutar lantarki ga babbar hanyar lantarki ta qasa wato *National Power* Grid a shekarar 1968! Garin Kaduna ya amfana sosai ta wannan gawurtaccen shiri, wajen samar da wutar lantarki ga masana'antu da mahalli.

Akwai matsololi guda biyu da ke tare da samar da wutar lantarki: qarfin wuta da kuma yadda za a rarrabata. A rahoton 1962, E.C.N na da qarfin lantarki da bai wuce "187 mega watts " ba. An samu qarin qarfin lantarki da ya ninka wannan sau talatin. A farkon shekarar 1964 tasoshin wutar lantarki a Kaduna na da qarfin 11.96mw. An kuma qara masu qarfi a shekarar 1965. Qarin buqatuwar lantarki, ya sanya qarin injunan ba da lantarki guda biyar. A wannan shekarar an qiyasce Kaduna za ta samu isasshen lantarki har na tsawon shekaru goma sha-biyar masu zuwa.

Garin na samun wutar lantarki ta hanyoyi guda biyu: ta hanyar manyan injunan ba da wutar lantarki wato "Generators. " Da ta babbar hanyar wutar lantarki ta qasa wato *National Power Grid*. Ana rarraba lantarki a garin ta hanyoyi

[1] MaxLock, *Kaduna*, shafi na 113.

ta kafa dogayen itatuwan lantarki a layukan wannan gari. *Max Lock* ya ba da shawarwari a riqa binne wayoyin lantarki a qasa saboda ya fi inganci da kyau.[1]

Filin Jirgin Sama na Farko

Filin jirgin sama na farko a garin Kaduna shi ne babban filin sukuwa da yanzu ake kira Dandalin Murtala ko "Murtala Square'. A wannan fili ne jirgin sama ya fara sauka. Jirgin sama na "Imperial Airways " ne ya fara sauka a garin Kaduna, a cikin shekarar 1925. Qananan jirage uku ake amfani da su a wannan lokaci. Sarkin Zazzau Ibrahim shi ne ya fara kawo ziyara a wannan filin jirgin sama, har ya shiga aka yi shawagi da shi.

Jiragen ba a amfani da su da daddare, da zarar Yamma ta yi sun daina zirga-zirga ke nan saboda rashin fitilun lantarki irin na zamani. Da rana lokacin da jiragen suke amfani, sai a turniqa hayaqi a wurare daban-daban a wannan fili saboda matuqin jirgi ya gane wajen sauka daga sama. Wannan hayaqi idan ya yi sama zai nuna wa matuqin jirgin filin sauka.

A haka aka riqa amfani da waxannan jirage kafin samuwar filin jirgin sama irin na zamani a garin Kaduna. A lokacin varkewar Yaqin Duniya na Biyu ne wannan fili ya havaka sosai saboda qasar Ingila ta yi amfani *da shi*, a matsayin wani wadabe da ya taimaka wajen jigular sojoji da kayayyakin yaki. Amfani da jirgin sama ya sauqaqa zirga-zirga cikin hanzari a wannan zamani. Ya kuma qara havakar hanyar sadarwa a tsakanin wannan gari da sauran garuruwa a cikin Nijeriya da Qetare.

Hanyar Mota Zuwa Zariya

Tun kafuwar garin Kaduna jama'a ke zirga-zirga bisa jakuna, da dawaki, da basukuri da motoci saboda hanyoyin mota a cikin gari sun gyaru sosai. Zirga-zirga tsakanin Kaduna zuwa Zariya bisa mota ba ta samu ba sai a qarshen shekarar 1919. Karamar Hukumar kuma *Local Authority* ta Zariya, ta xauko aikin hanya daga Zariya ta haxa da Sabon Birni . Ita wannan hanya ce ta haxe ta Fidaburdi wadda ta tashi daga Kaduna zuwa Rigachikun. An faro wannan aikin hanya ne da ranin watan Satumba, an kammala ta kafin qarshen shekarar 1919.

Buxewar wannan hanya ta qara sanya jama'ar garin Kaduna sun mallaki Basukuri da Motoci, don a tsakanin 1 ga Janairun shekarar 1920 zuwa 31 ga Maris xin shekarar 1920, an yi rajistar Basukuri guda xari da shittin da bakwai (167) da kuma motoci guda shida. Buxewar wannan hanya babban mataki ne na qara bunqasar sadarwa tsakanin Kaduna Jamsin da sauran garuruwa. Duk wani mai hali in ba ya buqatar bin jirgi, to, sai ya bi ta mota don hanyar ta buxe har zuwa Zariya.

---

[1] MaxLock, *Kaduna*, shafi na 122

An faxaxa hanyar mota wadda ta haxa Kaduna da Zariya a shekarar 1925. Ita wannan hanya mai nisan kilomita tamanin da biyar (85km), an kashe fam dubu xaya da xari shida da saba'in (£1,670). An samar da kuxin wannan aiki daga Baitulmali na Zariya.[1]

A kuma shekarar 1925 ne aka gina hanyoyin da suka haxa Kaduna da Rigacikun da Rikoka da Pambeguwa da Saminaka. A kusan wannan shekara aka inganta hanyoyin da suka haxa garin da Sabon Birni, da Birnin-Gwari da Dungurun. Babu shakka buxe waxannan hanyoyi, sun taimaka gaya wajen shigo da kayayyakin abinci zuwa garin Kaduna. Kammala aikin hanyar jirgin da ya yi Gabas, wato *Eastern Railway Project*, a shekarar 1927, ya taimaka wajen bunqasar xaukar kayayyakin gona da ma'adinai daga sassan Arewa zuwa gavar teku domin kaiwa qetare. A qarshen wannan shekara kuma an haxa garin Kaduna da garuruwa masu yawa da ke lardin Zazzau waxanda ke taimakawa wajen samar da da bunqasar sufuri da kasuwanci da abinci da zirga zirgar jama'a.

Harkokin Rayuwa

Garin Kaduna, gari ne wanda Turawa, da leburori da sojoji suka kafa qarqashin shugabancin Gwamna Lugga. Shi wannan Gwamna ya samu babban yabo saboda gano wannan waje da kuma xaukar xawainiyar kafa wannan gari da ya yi da hannuwa biyu.

Kamar yadda muka sani duk inda sojoji ko leburori suke, to, dole ne su qunshi qabilu iri-iri waxanda addininsu da al'adunsu suka bambanta da juna. Irin wannan zama ba zai yiwu ba in da babu shugaba nagartaccewanda zai tabbatar da ganin babu wata qabilar da aka danne, kuma wani addini da aka hana binsa. Tara leburori da sojoji qarqashin shugabancin Turawa sai ya zama kamar tsintsiya ce da maxaurinta xaya, matuqar babu wannan maxauri, to, duk tsintsiyar sai ta war watse a hankali. Haka yake a Kaduna inda babu Turawan mulki da wannan zaman gari bai yiwu ba, don kowace qabila ba za ta jure wa ganin al'adu ko addinin wata qabilar ba. Saboda haka a wannan gari 'yancin xan-Adam ya fara hudo kai a Arewa.

Dokokin da Turawa suka kafa wa wannan gari sun taimaka qwarai da gaske wajen maida wannan zama tabbatacce. Sabili da haka Kaduna sai ta taso da zaman lafiya, da tsabta tare da havaka cikin xan qaramin lokaci. A wannan gari babu wanda zai bugi qirji ya yi abin da ransa yake so, in har wannan abin zai karya dokar gari. Zuwan Turawa qasar nan abin da suka yi qoqari su yi hani da yinsa shi ne mulkin Ifriqiyya.

A cikin mulkin 'Ifriqiyya " ko kuma mulkin kama karya, shugaba yana iya sanya jama'a su yi wa mutum wasoso (wato a washe masa gida babu gaira babu

[1] NAK, Zarprof. 2872: *Annual Report of Zaria Province* for 1925.

dalili, muddin dai wannan shugaba ya buqaci yin haka). Irin wannan shugabanci da Turawa suka tarar ana yi a qasar nan sai suka yi tir da shi suna cewa ai shugabanci bai yarda da zalunci ba, in ana so a hukunta jama'a bisa shari'a sai a kafa masu dokoki, duk kuma mahaluqin da ya kuskura ya karya waxannan dokokin, to, sai a hukunta shi yadda shari'a ta zayyana.

Irin mulkin dimokuraxiyya shi ne suka nuna a wannan gari da suka kafa. Irin wannan mulki kuwa baqon abu ne a Arewa don haka saboda rashin fahimtar wannan mulki, shi ya sa jama'a ke cewa, "Kaduna Bariki ce sai ka yi abin da ranka yake so. " Wannan rashin fahimtar irin wannan mulki kuwa ya jawo wa mazauna garin Kaduna baqin jini. Muddin mutum zai faxi ra'ayinsa, ya nuna ya san haqqinsa ya kuma dage da ya ga ya kare su daga wurin hukuma, to, wannan abu fa babban aibi ne, wannan shi ne rashin kunya ko iskanci. Abin da aka sani a sauran qasashe kuwa a wancan zamani shi ne bin umarnin shugabanni ko da zaluncinka ake yi, don ba a san wani talaka da wani abu wai shi 'yanci ba. Abin da shugabannin suka sani shi ne jama'a (talakawa) su zauna kara zube, sai yadda hukuma ta sarrafa su don kuwa wannan shi ne ladabi da biyayya. Irin wanna mulki, ya kaucewa *koyarwar* Mujaddadi mutuqar gaske.

Idan jama'a qabilu iri-iri suka zauna tare a qarqashin hukuma xaya, saboda bambancin addinai da al'adu, dole ne su xauki matakan da za su bi don su zauna cikin lumana. Dole ne su rungumi qaddara su bar qyamar junansu, wannan zai yiwu ba sai in sun fahimci juna sosai.

Tunda wannan gari ya qunshi qabilu iri-iri, saboda haka sai qabilar wannan gari, ta xan bambanta da *'yar'uwa*rta da ke sauran qasashe. Misali, harkar rayuwar Bahaushen garin Kaduna ta xan bambanta da ta Bahaushe Kano da Zariya da Sakkwato da Daura da kuma Katsina ta fuskar halayya. Su Hausawan waxannan garuruwa sun sami damar tafiyar da al'adunsu kamar yadda suke so, 'ya'yansu kuma ba su gauraya da 'ya'yan wasu qabilu ba, don haka sai su taso da Hausa sosai kuma Hausa tsantsa tare da ingantaccija al'adun Hausawa. Su waxannan yara za su taso da qyamar waxansu qabilu da suka bambanta da ta su, duk wani abu wanda yake baya cikin tasu al'adar, to, wannan abu fa abin qyama ne.

Shi Bahaushen garin Kaduna kuwa, qaddara ta sa ya taso qarqashin shugabancin da dolensa ne kuma ya rungumi sauran qabilu don *zaman tare*. Har-ila-yau wajibi ne kuma yana ji, yana kuma gani, ya qyale sauran qabilu da al'adunsu. A wannan gari ne za ka ga kowa ya kama harkar *gaban shi*, Musulmi da wanda ba Musulmi ba suna zaune gida xaya. Idan zai tafi Masallacin Juma'a sai waxanda ba Musulmi ba su ce "a'a Wane, za ka tafi masallaci, to, sai ka dawo. " Haka kuma shi ma idan maqwabtan na shi Kiristoci ne, kuma za su tafi Majami'arsu, shi ma sai ya rama, "a'a Mista Wane za ka tafi Majami'a, to, sai ka dawo. " Ba kuma abin mamaki ba ne ka ga wannan gidan Musulmi ne, na gaba da shi gidan wanda ba Musulmi bane, mai yiwuwa ma wannan gidan ana sayar da

giya a cikinsa. Shi wannan Musulmi ba shi da damar hana sayar da ko shan giya a gidan maqwabcinsa muddin ba a shigo wajen mulkinsa ba.

'Ya'yan mutanen Kaduna kuma, sai suka wayi gari suka ga ai yawancin 'yan ajinsu a makaranta Yarbawa ne ko Ibo, sannan saboda rayuwar yau da kullum sai ka ga 'yan qabilu iri-iri sun yi rukuni-rukuni in sun taso makaranta ko kuma in za su tafi.

Saboda wannan cakuxuwa sai waxannan yara su taso da Hausa daban da ta qasashen Hausa, domin rashin samun damar nuna na su al'adu kamar na takwarorin da ke sauran qasashen Hausa. Hasali ma, Hausawan wannan gari sun qunshi mutanen garin Sakkwato da Zariya da Kano da Daura da Katsina, wannan abu kansa zai sa waxannan yara su taso da ta su Hausar.

Misali idan Basakkwace zai ce da haqori 'Haure', BaKano ko Bakatsine zai ce da shi, "Haqori, to, sai su yi wa kansu zavi da sunan da ya fi sauqin faxi. Saboda haka sai Hausar ta su ta kusa qunsar duk karin Hausa iri-iri, wanda in mai saurare ya ji, bai iya cewa mai wannan mai magana ga qasar da yake. A taqaice dai zaman wannan gari ya vullo da wata irin Hausa wato "Hausar Kaduna. "

Kalmar Turanci ta gurvata Hausar mutanen Kaduna. A lokuta da yawa Hausawan wannan gari su kan sami qabilar da ba ta jin Hausa sai Turanci, turancin ma burokin. Wannan abu ya tilasta wa jama'ar wannan gari amfani da kalmar turanci ko da ta burokin cewajen magana da zance. Fahimtar wannan abu zai rage qyama da wulaqancin da su Hausawan Kaduna ke gani, idan suka tafi gururuwa a Arewa.

Misali, an xauki rayuwa in ba irin ta sauran qasashen Hausa ba, rayuwar banza ko da wannan rayuwar na bisa qa'idar Addinin musulunci. Rayuwar mutane na canjawa, idan an canja masu yadda za su tafiyar da harkokin yau da kullum, amma usulin waxannan mutane ba zai sauya ba. Su Hausawan Kaduna waxanda galibinsu su ne suka kafa garin Kaduna, suna zaune ne zama irin na jama'ar leburori da tsofaffin sojojin da suka kafa wannan gari na Kaduna, sun bai wa zuriyarsu abubuwa guda biyu da za su faxa wa duniya. Na farko dai leburori ne suka haxe, ko kuma suka xinke Nijeriya xaya a lokacin tana qasashen-qasashe, sun xinke wannan babbar qasar tasu da hanyar jirgi. Ita wannan hanya ce ta kawo haxe Arewaci da kudancin Nijeriya da aka yi a cikin shekarar 1914. Gumin waxannan bayin Allah Ya taimaka qwarai da gaske wajen havaka arziqin Arewacin Nijeriya da sauran vangaren Nijeriya baki xaya.

Abu na biyu kuma shi ne, sojojin da suka yi yaqunan duniya, sun fitar da qasar Nijeriya a idanun duniya baki xaya, sun yi bajintar da ba za a manta da ita ba a cikin tarihin yaqoqin duniya. Galibin waxannan sojoji 'yan Arewa ne. Bajintar waxannan bayin Allah ba za a nisanta da ita ba, don har yanzu 'yan Arewa na cin albarkacin waxannan bayin Allah.

Daga qarshe kuma su waxannan bayin Allah sojoji da leburori tare da Nasara sun kafa garin Kaduna, sun kuma taimaka wajen havakarsa. Saboda haka rayuwa a Kaduna, ba rayuwa bace mana tushe. Amma rayuwa ce ta usuli mai kyau saboda haka ne garin Kaduna ya taso cikin sala da nasara, har yanzu kuma yake cikin sa'a da nasara! Don haka ne Sheikh Ibrahim Nyass, ya albarkaci wannan gari saboda ya ce: "Kaduna, *La Bi Dun*! " a harkar ilimi ne aka bar Kaduna a baya. Arewa ce baki xaya take baya-baya a harkar ilimin boko, saboda irin fasalin yadda aka kawo, a kuma yaxa shi a Arewa. Tarihin ilimin bokon Arewa yana da muhimmanci sosai saboda fahimtarsa ne zai taimaka wajen fahimtar matsalolin da suka dabaibaye shi a wannan zamani. A dalilin haka ne za a kawo xan taqaitaccen wannan tarihi.

Ilimin Boko da Tasirinsa

Ilimi abu ne guda mai rassa wanda kowane reshe babu wanda ya san shi sosai sai wanda Allah Ya sa ya duqufa cikin wannan fanni. A kowane rukuni ko sashe na jama'a ana samun masana fannoni daban-daban waxanda xalibai za su keve kansu don su yi fice a waxannan fannoni. Waxansu su xauki hanyar zama likitoci, waxansu Injiniyoyi, waxansu masu shari'a, wato Lauyoyi, waxansu koyarwa, wato Malamai, kai ga su nan kowane vari aka kama sai a yi ta yi har a sami daraja a kan wannan fanni wato Digiri, a cikinsa. Kowa kuma a kan wannan reshen da ya kama ne zai yi ta tafiya har ya zama shaihi a ciki, wato Farfesa, har kuma ya qare rayuwarsa a kai.

A dalilin haka ne ake son kowace al'umma ta samu masu ilimi masu yawan gaske kuma a fannoni iri-iri na rayuwar xan-Adam. Domin kowa a varinsa shi ne Malam kuma shi ya kamata a saurara wa don a amfana daga ilimi da qwarewarsa, a kuma dogara da shi a matsayinsa na tubalin ginin al'umarsa. Kamar yadda tubali yake a wajen gini, haka yake ga al'ummarsa. Komai ilimin mutum da anda ya fi shi, saboda haka ake son mai ilimi ya riqa qara iliminsa ya riqa kuma sabunta fannin iliminsa don kuwa kowane mai ilimi yana da malami a sama da shi.

Duk abubuwan da Allah (S.W.T.) Ya halitta a doron qasa ya sauqaqe ma mutum ya kuma maida su kamar kayan aiki masu amfani ga rayuwar xan-Adam, alal misali, dailimin Kimiyya da Fasaha ne zai ci moriyar waxannan halittu, da ya samu, yake gani da ma waxanda yake tsammani zai iya gani. Haka kuma Alla Ya baiwa 'yan-Adam basira, haziqanci da fahimtar abubuwa cikin hanari. Saboda haka babu wani jinsi na xan-Adam da ya fi wani jinsi wajen halittar qwaqwalwa da basira, duk dai-dai suke. Qwaqwalwar Bature ba wai ta fi ta Baqar Fata ba ne, amma inda aka bambanta shi ne wajen al'adu da xabi'u da yanayin wajen zama.

Arewa ta yi suna wajen ilimi da fasaha shekaru aru-aru kafin shigowar Turawa Arewa. Amma da Turawa suka zo sai suka shimfixa ilimin boko ta yadda zai zama wata kutungwilar hana ta ci gaba. Domin a wajen bada wanna ilimi sai

suka rarraba kan jama'a kamar yadda suka same ta, saboda kada ilimin boko ya zama wani sinadarin haxin Kan Jama'a. a maimakon haka, sai ilimin ya zama wata dama ta nuna fifiko da rarrabuwar kawunan Jama'a, don a sami wani a sami wani sashen jama'a ya danne wani sashenta. A duk inda ake koyar da karatu ana haxa 'ya'yan kowane sashe a aji guda domin su taso da zumunci da son juna da kuma kishin al'ummarsu, ba kishin kansu ko na gidajensu ba.

Abin takaici shi ne, da Turawa suka fara bada ilimin boko sai suka qi bin wannan sahihiyar hanya sai suka kafa sashen jama'a ya zama ajalinsu na karatu. A wancan lokaci kuwa suka raba al'umma zuwa gidaje uku: Sarauta, Malamai da Talakawa. Kowane gida aka gina shi don ya kare gidansa, 'ya'yansa kuma su yi qoqari wajen ijganta shi ta ji da kai da nuna isa.

Saboda 'ya'yan talakawa ba za su sami ilimi da horon zama Injiniyoyi ko Likitoci ba. Haka kuma 'ya'yan Sarakuna ba za su zama Likitoci ko Injiniyoyi ba sai dai su shahara a fannonin shugabanci. Babu kuma yadda za a yi talaka ya zama shugaba domin ba shi da wannan horon, don haka ba zai sami wannan damar ba. A wannan tsari sai Turawa suka qagama wa al'ummar Arewa wasu ajujuwa da qarfi da yaji, ba da ilimi, qwazo, haziqanci da cancanta ba. Suka kuma maida ilimin boko ba na duk jama'a ba sai xan wane da wane.

A zuwan Sir Percy Girourd a shekarar 1907 sai maganar bada ilimin boko a Arewa ta taso da qarfi sosai, batare da bata lokaci ba sai ya naxa Mr. Hanns Vischer Daraktan ilimi ya kuma umarce shi day a tsara shirin bada ilimi samfurin wanda Lord Cromer ya aiwatar a qasar Masar. Amma wannan sabon Darakta sai ya gay a kamata a yi nazarin tsarin na wasu qasashe don aga ko irin tsarinsu zai dace da Arewa. A dalilin haka ne ya ziyarci makarantun Ikko, da Gwalkwas (Ghana) da Kwalejin Gordon *Memorial College* dake Khartum ta qasar Sudan.[1]

Amma saboda wasu dalilai da ba'a bayyana su ba, sun sa wannan shugaba bai bi umarnin da aka bashi na farko ba. Domin bai shimfixa hanyar bada ilimi irin na qasar Masar ba. Shugaban ya aiwatar da tsarin ilimi da zai kawo matsala babba ga Arewa. Saboda Turawa na cike da fushi da 'yan Arewa domin sun yaqe su sun kuma qi kai da fata a riddad dasu wato su zama Kirista. Bilhasali ma dai mulkin mallaka bai zo don ya havaka wata qasa ba, illa wannan mulki ya tsotse lemu ya jefar da fata. A dalilin haka ne yadda za'a baiwa Arewa ilimi ya sanya Turawan Mulki cikin zuzzurfan tunani. Ya zama wajibi a yi amfani da ilimin boko a mayar wa Arewa da martani mai mummunar illa.

---

[1] Charless Orr, Making of Northern Nigeria, shafi na 267

Da wannan niyya ce Mr. Vischer ya kafa harsashin yaxa ilimi na farko a Nasarawa dake kusa da birnin Kano cikin watan Agusta 1908. Kafin watan Satumba wannan Makarantar Boko wadda ake kira Makarantar xanHausa sai ta fara bunqasa. An kafa wannan Makaranta ne a wajen da ke mil xaya kafin a kai birnin Kano kuma mil biyu ne tsakaninta makarantar da gidan Razdan. Sir Charles Orr ya cewannan waje ya dace sosai da kafa makaranta saboda ba shi kusa da hargowar jama'a da kuma mutane vatagari. Sa'anan kuma ba ta yi nisa da fadar Sarki ba, ga ta cikin gari amma nesa da jama'a.

Abin takaici shi ne illar wannan makaranta yana ga irin karantun da aka baiwa xalibai da yadda aka basu karatu da horo. Domin a qirqiro wata al'umma wadda zata rarrabu ta kan shashe shashe ko ajujuwa sai xan Hausa ya kafa makantarsa mai kamfawul guda babba wanda yake xauke da makarantu ko ajujuwa da suka rarrabu ta matsayi da nasaba amma ba ta haziqanci da qwazo ba akwai ajujuwa uku a cikinta, sune:

i. Ajin 'ya'yan Sarakuna
ii. Ajin koyon malanta
iii. Ajin koyon sana'a da Harsuna[1]

Idan aka yi nazari sosai za'a ga ta waxannan ajujuwa ne aka assasa, raba kan al'umma zuwa ajujuwa uku Sarakuna, ma'aikata da talakawa waxanda suka ta so suna gaba da hamayya da juna wajen gina kansu da ajujuwansu ido rufe. Soboda ko da 'ya'yan wannan makaranta suna cikin kamfawul guda ne amma kowane xalibi yasan matsayinsa, da darajarsa. Domin a dasa qwayar haddasa da gaba a zukatan 'yan bokon Arewa ne aka shimfixa wannan tsari wanda kuma ya yi mummunan tasiri akan al'ummar Arewa. Saboda babu wani dalilin da zai hana a haxa 'ya'yan Sarakuna da ya'yan malamai da attajirai da talakawansu a aji guda ana basu darasi kamar yadda ake yi a sauran wurare. An qi yin haka ne saboda a raba kawunansu a kuma assasa gaba da rashin jinqai a tsakaninsu. Saboda waxannan dalilai ne ba'a xauki kiristoci a wannan makaranta ba sai Musulmi kawai, su kiristoci an haxa kansu waje guda ana ba su ilimin tarbiyar da tausayi da jinqan jama'a don neman rahamar Ubangiji. Wato an haxa ilimi da koyarwar addinin Kirista.

---

[1] Charless Orr, Making of Northern Nigeria, shafi na 267

Ta wannan tsarin bada ilimin boko ne a cunkusa bingiren Hindu wanda da Turanci ake kira, *Hindu Caste System* a fakaice kuma tsarin ana ce ma Jajmani *System* wato jajmananci. A tsarin Hindu, al'umma ana raba ta ne bisa darajar tsatson da mutum ya fito wanda ake samu ta haihuwa kawai ba ta bisa ilimi, qwazo da nuna bajinta ba. A qasar Hindu tsarin *Hindu Caste System* ya haifar da gidaje kamar haka:

i. Brahmins ajin limamai da masana;
ii. Kshatriya ajin 'yan sarauta da barade;
iii. Vaishyas gjin manowa da 'yan kasuwa;
iv. Shudra ajin masu wanki
v. *Untouchables* ajin qasqantattu bayin Allah marasa galihu.

Manufar makaranta ta uku wato *Technical and Vernacular Schools*, shirne *koyar da* ayyukan sana'o'i, 'yan wannan makaranta kuma su kan sami 'yan awooroi da ake koyawa masu harsuna. . . [1]

To, wannan tsari sai ya yi kama da na *Hindu Caste System*, amma bambancinsa ta ilimin boko aka raba kan al'umma amma ba ta haihuwa ba. Don haka tsari ne da ya raba jama'a ta sana'o'i wato jajmani system ko jajmananci. Don haka ne tsarin yaxa ilimin boko a Arewa ya bambanta da na ko'ina a Nijeriya domin yana da tsari irin na rayuwa a qasar Indiya. Irin wannan tsari ne ake so ya kafu a Musulmin Arewa ba domin komai sai wannan tsari na *Hindu Caste System* yana hana al'umma ci gaba. Saboda haka ne ilimin boko a Arewa ya zama wani tarnaqI ne na hana ci gaba. Yau shekara xari da kafa shi amma har yanzu Arewa bata ci gaba ba kamar yadda ake buqata.

Da harshen Hausa ake koyarwa a waxannan makarantu. Wannan tsari ya bauxe wa tsarin bada ilimi na asali wanda aka sani a Arewa. Saboda ilmi kyauta ake bada shi. Ko da makarantar xanHausa ta fara qasaita sosai sai aka kafa.

Sir Charles Orr ya bayyana dalilan kafa wannan shiri na yaxa ilimin boko ga Musulmin Arewa, inda ya ce:

Manufar kafa Ajin 'Ya'yan Sarakuna ko *Chiefs' Sons School* shi ne domin a baiwa 'ya 'yan Sarakuna da shugabanni horo wanda zai sa su dace da riqe

[1] Charless Orr, Making of Northern Nigeria, shafi na . 267 - 268

muqaman mulki. Wannan makaranta ta qunshi 'yan sarauta da danginsu, tana kuma xaukar yara 'yan shekara takwas zuwa goma sha takwas.

Manufar Ajin Koyan Malanta ko 'Mallamai School' shi ne ta bayar da horo ga malaman dukkan makarantu da matanen da za su yi aikin rubutu na akawu da safiyo a qarqashin En'e ko jami'an Turawa.

An daxe ana kambama waxannan makarantu wajen bada ilimin zamani da sana'o'i irin na Turawa. Wataqila akan cusa masu ra'ayi da hanyoyin kare kansu da ajujuwansu da ake sasu ta yin aiki Tuquru. A dalilin haka ne har akwai 'ya'yan Sarakunan da a ke raka su makarantar da kaxe-kaxe da bushe-bushe. Kuma aka ce don sha'anin ilimi ya sami karva ne a Arewa aka yi haka. Shi ya sa aka kula da jin daxin zaman almajiran nan, ba a son abin da ya tava su.[1] Hasali ma dai a wannan lokacin, xalibai da yawa da matansu suke zaune.

Abdulmaliki Mani ya ce, a wannan Makaranta ana *koyar da* ilimin noma har ma akwai lambu musamman don almajirai su sami iliminsu ta hanyarsa. Akwai kuma nuna ilimin sana'o'i, ana koya wa almajirai yadda za su zama masu sana'a qwaqqwara. Kusan ma a nan Arewa dai duk irin sana'o'in da a ke yi, galiban in dai mutumin Arewa ne ka gani na yin kamar sassaqa, ko ginin birkila, ko shafa sumunti, to, in ka bi sawu sai ka tarar, ko ya tava shiga makarantan nan, ko kuma ainihin wanda ya koya masa a Kano ya koya.[2] Duk da kambamawa da ake wa wannan makaranta kada mu manta Arewa ta yi suna wajen aikin gona, gini da sana'a shekaru aru-aru kafin zuwan Turawa. A wannan zamani kuma babu tasirin sana'o'i. Amma saboda ba'a shimfixa harsashin koyar da ilimin sana'a da noma don su tafi da zamani ba sai tsarin ya rushe kamar rumfar kara.

A hankali sai yan Arewa suka yi watsi da sana'o'in da suka gada na gargajiya saa'nan suka yi wa na Turawa xaukar sakainar kashi. A dalilin haka ne sana'a ta kusan mutuwa murus a Arewa a wannan zamani. Kamar yadda ilimin sana'a bai yi tasiri ba haka ilimin boko ma bai yi tasiri a Arewa ba. Domin ilmi ne dake cunkusawa Musulmi halin Hindu. Amma hali ba ta nau'in ibada ba ta kare aji da bautar nasaba da nuna wariya fariya da alfahari da jin kai ga jama'ar dake qasa da ajin mai wannan ilmi ga mutum sai tausayi da taimakon jama'arsa ya yi kaxan. Inda kuma ilimin ya yi yawa.

---

[1] Abdulmaliki Mani, Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa, shafi na 214

[2] *Ibid*, shafi na . 267 - 268

A tarihin Arewa, ilmi kyauta ake bada shi. Amma sai aka sanya biyan kuxin makaranta a wannan lokaci. A ran 1 ga Nuwamba 1910 aka fara biyan kuxi a makarantar boko kamar haka: 'Ya'yan Sarakuna su ne za su biya sule bibbiyu kowane wata. Masu koyon aikin malanta suna biyan sule sule. Masu koyon sana'a su ke biyan sisi. Haka kuma kuxin sham magani shi ma sisi ne.[1] A za kuxin makaranta ya rage shigar yara da yawa wannan makaranta domin ba kowane ya ke da arzikin biyan waxannan kuxaxe ba.

Waxannan ajujuwa uku sai suka bunqasa a hankali suka kuma zama Qananan Duniyoyi masu hamayya da gasa da juna. Saboda haka ne wannan ilmi ya assasa hamayya da tazara tsakanin 'yan Sarakuna masu mulki da Malamai masu koyarwa da masu koyan sana'a. Kowane aji yana ji da kansa wajen nuna wata isa da daraja da iliminsa ya ba shi. Don wannan tsari ya kafu sosai sai Turawa suka qi faxaxa shi tun. Tun da aka kafa makarantar Xan Hausa a 1909 ba a sake kafa wata ba sai bayan shekaru goma aka kafa kwalejin Katsina a 1921. Har'ila yau ba'a yarda a sauya wannan tsari ba sai bayan shekara talatin. A waxannan shekaru tsarin ya kafu sosai tasirinsa kuma ya yiwa Arewa mummunar kamu.

Turawan Mulki sun san Arewa za ta fuskanci matsalar ilmi don haka suka mayar mata da wannan martani. Suka qi sanya 'ya'yan Kirista a wannan makaranta. Don za a raba kawunan Musulmi da Kirista a shekaru masu zuwa. Bayan an rarraba kan Musulmi ta basu ajujuwa daban daban. A wannan tsari 'ya'yan Sarakuna ba ruwansu da koyon sana'a sai mulki. A irin wannan tsari ne 'ya'yan attajirai suka riqa gudun makaranta saboda ya'yan Sarakuna na dukansu. A dalilin haka ne Sarkin Kano Abdullahi Bayaro ya kafa makarantar 'ya'yan attajirai a birnin Kano a shekarar 1928. Firimiya shi kansa tsohon xalibin kwalejin Katsina ne ya aibanta wannan tsari.

Banda cunkusa halin Hindu a zukatan Musulmi, wannan tsari kuma shi ne ya yaxa baragurbin ilimi ga Musulmin Arewa. Domin kuwa wasan kura Turawa suka riqa yiwa wannan shiri na bada ilmi. A wajen bayyana wannan illa, Alhaji (Dr) Abubakar Imam ya ce:

"Mutane babu wanda za su yi kuka da su sai Turawan mulki. Dalili shi ne Turawa sun ruxi. Arewa saboda har zuwa 1932, biyayya ita ce babban abin da ake koyarwa a makarantun Arewa. A Kwalejin Katsina biyayya da hali na gari, suna

[1] Abdulmaliki Mani, Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa, shafi na . 267 - 268

gaba da haziqanci da fasaha. Sune kuma abin dubawa wurin bada takardar shaidar fita makaranta. Ba a bada jarrabawa. Ya bayyana cewa Rukuni na farko wanda suka fito daga Kwalejin ba a basu jarrabawar fita makaranta ba. Tun da ya ke babu jarrabawa babu yadda za acewane ya ci ko wane ya faxi. Daga fara Kwalejin har zuwa 1932 babu xan Kwalejin Katsina da ya sami wata takardar shaidar fita makaranta.[1]

Alhaji (Dr.) Abubakar Imam tsohon xan kwalejin Katsina ne kuma mashahurin mutum ne wanda ya yi fice a harkokin ilimi da shugabanci a Arewa. Ya kuma fahimci mulkin mallaka da *Indirect Rule* sosai da sosai. Saboda haka ya san kitso da baqin zaren da Turawa suka yiwa Arewa. Amma su Turawa ba su xauki cewa sun yaudari Arewa ba, don sun maida mata wani mummunan martani ne a fakaice. Domin kuwa sun yi ta qorafi da yaqinsu da kuma qin karvar addininsu.

Waxannan dalilai suka sa suka maida martani mai muni da illoli masu yawan gaske. Don haka harsahin da aka kafa tushen ilmi a Arewa baragurbine. Ga makarantun boko amma ba a *koyar da* ilimin boko a cikinsu. Editan ya ce: "Na rantse da Allah tushen mulkin qasan nan – biyayya – a sannu tana wargajewa. An sha gayawa almajirai su yi biyayya ga shugabanni, su gaida shugabanni, saboda waxannan ne hanyoyi na cin gaba. Yaran sun yi waxannan abubuwan kuma suna kan yin haka. Har ma akwai wasu masu zurawa aguje in sun ga malamansu su je su gaishe su. Duk sun sami takardar shaida wadda a ciki an rubuta "Kyaun Hali (Maki 50; Iya aiki maki 50). Wai har da irin wannan maki ne wasu suka sami daraja ta xaya.

Su 'yan makarantan da suka gama daga baya sun gane wofintakar wannan takardar shaidan. An fara jarrabawa a Katsina a shekarar 1933 amma ko shi ma ba shi da wani amfani in an fita jihar Arewa. Maimakon a gina mana jami'a sai aka shirya mana karatunmu na Jihar Arewa kawai. A cikin 1942 ne a Kwalejin Kaduna aka fara xaukar jarrabawa ta qasar Waje.

Saboda haka da ilimin da hanyar da aka bada shi duk sun yi mummunan tasiri Ta hanyar bada shi ne aka cunkusawa 'yan Arewa Halin Hindu. Firimiya Sir Ahmadu Bello ya yi alhinin irin tsarin bada ilimin boko a makarantar XanHausa da Kwalejin Katsina domin haka ne ya ce: "In dai ban da barebari, dukammu harshen Hausa, ya haxe mu mun zama abu xaya, ga mu kuma duk Musulmi. Babu

[1] Haroun Al-Rashid Adamu, shafi na 32

waxansu da suka zo daga wuraren da ba na Musulmi ba cikimmu. A yanzu ina ganin kamar yin hakanan kuskure ne, da abin da ya fi shi ne a sami kowa ne irin jinsi a Kwalej xin. Kuma ko ta yaya dai, da ya kyautu kuma a yi wata Kwalej xin wadda ba ta Musulmi ba, amma shi Gwamna Sir Hugh Clifford ba manufa tasa ke nan ba. Abin da ke cikin zuciyarsa, shi ne a sami Kwalej da dama na ya'yan Sarakuna, a zatona kamar irin waxanda mutanen indiya su ke da su.[1]

Kowa ya dubi tsarin yaxa ilimin boko a Arewa zai ga ya yi kama da na mutanen Indiya ne kamar yadda firimiya ya zata. Amma a Indiya xin ma ya fi kama da na mabiya addinin Hindu, wajen nuna wariya da bambanci a tsakanin jama'a. Turawan mulki ba su sanya Kiristoci cikin wannan makaranta ba saboda sun san wasan kura za su yi da 'yan Arewa ba za su basu ilimin boko ba. Amma ko a wancan lokaci tsarin ya sha suka da takori daga jama'a. Sarakuna sun nemi a kafa makarantun boko a manyan birane musamman waxanda da ke nesa da Kano kamar Barno amma sai Turawan mulki suka qi. A kabar makarantan xanHausa tilo a duk faxin Arewa har na tsawon shekara goma. Bugu da qari an daxe ana zargin Sarakuna da kawo wa Arewa wannan baragurbin tsari saboda rashin sanin cewa Turawan Mulki ne suka garqama wa Arewa shi saboda wata mummunar manufa. Sarakuna sun yi qoqari gaya su ga an faxaxa ilimi an kuma sauqaqa shi amma abin ya faskara.

A duk lokacin da aka ne mi karin makarantu sai Turawan Mulki su ce babu isasshen kuxin da za'a tafiyarda su. A dalilin haka ne Sarkin Kano Abbas ya umurci Baitil-mali qasarsa ta riqa bada fam dubu (£1000) a duk shekara don a tallafi Hukumar yaxa ilmi a Arewa. Haka kuma aka rika yi. Amma abin takaici daga cikin waxannan kuxaxen da ake samu daga qasashen Musulmi ne Turawan mulki suka raya makarantun Mishan a Arewa. Saboda Gwamna Lugga ya ga Turawan Mishan za su yi wa qasan nan amfani, tun ma ba a wajen qabilun da aka samu ba su da addini ba. Tun a wancan lokacin ne, saboda ganin yadda su ke taimako, Gwamna Lugga ya ba da shawarar lalle ya kyautu a riqa taimakon Mishan daga cikin abin da gwamnati ke samu don yaxa ilmi.[2]

Ta hanyar yaxa ilmi gwamnatin Lugga ta kashe tsuntsaye biyu da dutse guda: ta dankwafe ilimi a cikin Musulmi ta kuma yaxa ilmi mai zurfi ga qananan qabilu waxanda suka amshi addinin Kirista. Saboda shirin sabuwar Arewa dake

---

[1] Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 33

[2] Abdulmaliki Mani, Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa, shafi na 215

ta fe "na gaba ya koma baya", qananan qabilu su xauki jan ragamar mulkin Arewa saboda zurfin iliminsu, da kwArewar sana'o'in zamani. Wannan shiri kuwa ya yi tasiri saboda Musulmi masu halin Hindu sai suka taimaka wajen maida Musulmi koma-baya a harkar ilmi, domin ajujuwansu su dauwama a mulki da qarfin arziqi. Amma illa mafi muni da gwamnatin Lugga ta haddasa shi ne na wargaza makarantun allo a Arewa. Tun da ba sa cikin ajujuwan Makarantar XanHausa sai gwamnati ta yi watsi da su. Duk kuma mai xaukar rubutu daga dama zuwa hagu Jahili ne ba ruwan gwamnati da shi. Sai dai ya yi bara ya ci abinci. Musulmi masu halin Hindu suka amince da tsarinsa wanda har yanzu shi su ke bi.

A cikin 1900 Lugga ya faxi cewa akwai Makarantun Alqur'ani dubu ashirin (20,000). xaliban waxannan makarantu kuma sun kai yawan dubu metan da hamsin (250,000). A lokacin da ake shirin yaxa ilimi sai aka yi amfani da malamai da Alarammomi da ke waxannan makarantu. Sune suka fara riqe muqaman kashiyoyi, akawuna da ma'aji a ayyukan gwamnatin Arewa saboda iliminsu na rubutu da karatu da ajami. An yi amfani da su a ofishoshin mulki da ofisoshin kuxi har na tsawon wani lokaci kafin a fara fidda 'yan Makarantan xanHausa su maye gurbinsu. To, bayan da aka tsotse lemu sai aka yi jifa da fata. Saboda haka sai ace an ci amanar makarantun Alqur'ani da Alarammominsu. Don kuwa da aka ci gari da su ko kuturun bawa, ba'a basu ba. A maimakon haka sai aka tarwatsasu. A tsarin ilimi wanda gwamnati ta amince da shi wanda Turawan Mulki suka shirya wa Arewa babu Makarantun Alqur'ani a cikinsa. Haka kuma ba a xauki ilimin Addinin Musulunci da muhimmanci ba tun daga zamanin Lugga har yanzu. A dalilin haka ne miliyoyin almajiran waxannan Makarantu aka barsu cikin hutanci da qasqanci saboda tsarin Musulmi da halin Hindu ya maida su "Untouchables".

Firimiya Sir Ahmadu ya fahimci irin tsarin da Arewa ke bi wanda yake da haxari sosai. Ya kuma yi namijin qoqarin ya ceto Makarantun Alqur'ani daga cikin mummunan tarkon da Turawan mulki suka kafa masu. A cikin 1964 gwamnati ta yi alqawarin bada ₦300 ga kowace qaramar hukuma idan wannan hukumar ta yi na'am da makarantur Alqur'ani guda. Idan qaramar hukumar tayi ma'am da makarantun Alqur'ani, watau gwamnati zata bata ₦600. Su waxannan kuxaxe za a yi amfani da su ne wajen sayen kwanonin rafin xaki da bangon rufi da sumuntin shafe amma ainihin bangon gini na makarantar jama'ar garin ne zasu gina ta hanyar taimakon kai da kai. Kowace shekara kuma gwamnati ta yi alqawarin zata bada ₦50 ga kowace karvavviyar makarantar Alqur'ani. ₦20 daga

cikin ₦50 xin nan sadaka ce ga malam, sauran ₦30 kuwa saboda malam ya sayi allon bango, alli da sauran kayan aikin makaranta. Ita kuma qaramar hukuma zata bada nata gudunmawar ₦6 ga malam kowace shekara.

Abin baqin ciki ne wannan shiri wanda ake tsammani zai rayar da makarantun Alqur'ani, ba'a tafiyar da shi dai dai ba, bugu da qari, kuxin da aka ce za'a bayar ma sun yi kaxan saboda haka makarantun basu da alamar ciyarda kansu ga.[1]

Turawa sun kawo zamanin da Musulmi za suqi makarantar Alqur'ani. Qiyayyar Makarantu Allo shi ne illa mafi muni da Turawan mulki suka barwa Arewa. Musulmi ke qin makarantun Alqur'ani to, ya ya wanda ba Musulmi ba zai ga waxannan makarantu? Wannan mummunar martani ne da ya ruguza ruhin Arewa baki xaya. Har yanzu wannan qiyayyar na nan sai dai ta sake sabon salo. To, menene dalilin qiyayya da waxannan makarantu da Musulmi ke yi? Wannan qiyayyar tasomo asaline daga Turawan Mishan, waxanda suka lura da cewa da wuya a auya wa xaliban waxannan makarantu alqibla. Saboda haka gwamnatin mulki ta daqile ta da kuma tarwatsa su a hankali, bayan ta yi amfani da Alarammomi wajen ayyukan mulki.

Sardauna Sir Ahmadu ya yi qoqarin ceto waxannan makarantu amma saboda tsarin mulkin mallaka Arewa ke bi sau da qafa sai bai kai ga nasara ba. Abin da Gwamnti mai adalci za ta yi a yanzu shi ne ta amince ilimin Addinin Musulunci yana da muhimmanci kuma haqqin yaxa shi ya rataya ne akanta kamar ilimin boko. A dalilin haka ne makarantun Alqur'ani za su sami haqqinsu ba daga fi sabilillahi na jama'a ba, daga aljihun gwamnati. Alarammomi da manyan malamai dake koyarwa a Tsangayu da Zaure za su karbi albashi cikin daraja da mutunci kamar na masu ilimin boko. Albashin kowane mutum ya dace da zurfin ilimi da qwarewarsa. gwamnati na iya dora Harajin Allo a kan kowane Musulmi domin ta samu isassun kuxaxen qwato makarantun Allo da almajirai daga hutanci da qasqancin da suke gani a wannan zamani. Ko shakka babu halin da waxannan bayin Allah ke ciki, abin kunya ne ga Musulmi yak axe in har shi ne zai ci amanar Littafi mai Tsarki.

Wannan illa ita ce mafi muni da mulkin mallaka ya haifar a Arewa. Idan aka yi nazarin halayen mutane don a bayyana tasirantuwar wannan ilimi a kansu, za a iya yin hasashe ko Nazariyya da za ta bayyana dangantakar halayyar mutane don tasirin ilimin da suka samu. Wannan hasashe, Nazariyya ko *Theory* qoqari ne ko bincike wajen bayyana halin da mulkin mallaka ya cusa wa mutane a Arewa.

---

[1] Haroun Al-rashid Adamu shafi na 38

Nazariyya a Kan Zamantakewa a Arewa

Mulkin mallaka ya zo ya sami tsawo kusan shekara hamsin ya bar Arewa da illoli masu yawan gaske, har tsawon shekara hamsin. Ana iya ganin waxansu a zahiri waxansu sai an yi tunani mai zurfi a gane su. Waxannan illoli sun taru sun sauya tunanin xan Arewa. Sun kuma raba al'ummarta kashi kashi masu hamayya da gaba da juna wajen neman wanzu wa. A dalilin haka ne na gabatar da nazarori wato *Theories* guda biyu waxanda za su taimaka wajen haskaka tasirantuwar waxannan illoli a kan al'umma da nufin a yi maganin su. Ga nazarorin kamar haka:

1. Ilimin Boko a cikin Musulmin Arewa na cunkusa masu halin Hindu. Sa'an nan ilimin yana qara yawa taimako da tausayin al'umma na qara raguwa.
2. An kasafta al'ummar Musulmin Arewa zuwa azuzuwa kwatankwanci na *Hindu Caste System* ta qasarsa Indiya.

Idan mutum ya yi tunani a kan nazariyar farko zai ga yadda aka kafa makarantar Boko a Birnin Kano a 1910, haka jama'ar Arewa ta koma. Kowa ya taso ne da son kansa, zuri'arsa da abokan hulxarsa wato 'yan ajinsa a al'umma. A dalilin haka ne sai ilimin Boko ke qara tsada a cikin Musulmin Arewa a kullum domin da shi ne mutum zai iya fita daga wani aji zuwa aji mafi daraja kamar yadda haihuwa ke sauyawa mutum darajar matsayinsa a *Hindu Caste System*. Alalmisali, *Untouchable* wanda shi ne qasqantacce a cikin wannan al'umma, idan ya haqura da qasqancin rayuwa, hutanci da talauci, to, idan ya mutu, ana iya haifarsa ya dawo a wani aji mafi daraja kamar na *Brahmins*.

Shi kuma wanda yake cikin ajin *Brahmin* idan ya qi bin addininsa yadda ya kamata a wannan rayuwa, idan ya mutu ana iya haifarsa a ajin *Untouchables* inda zai xanxana kuxarsa. Saboda hisabi a duniya ake yinsa ta a mutu a dawo wato *Reincarnation*.

A addinin Hinxu babu sakamako da Wuta ko da Aljanna. Saboda addinin bai yarda da tashin Qiyama ba. Idan mutum ya aikata alheri idan ya mutu sai ya dawo ta hanyar *Reincarnation* a aji mafi daraja inda zai more rayuwarsa. Idan kuma sharri mutum ya qulla a wannan rayuwa, idan ya mutu zai sake dawowa zuwa aji maqasqanci inda zai sha wuyar rayuwa. Saboda mugun abin da ya shuka a wancan rayuwar da ta wuce ita yake girba a wannan sabuwar rayuwar. Saboda

haka sai taimakonsa ya haramta domin alhakin da ya xauka a waccan rayuwar tasa da ta wuce shi zai girba. To, ya dawo ya na xanxana kuxarsa, wane taimako za ka ba shi?

Amma wani lokaci idan mutum ya mutu yana aikata mugun abu, a wata rayuwa in ya mutu sai ya dawo ciki sifara wata dabba kamar kare ko alade ko gafiya. Saboda haka dabbobi, tsuntsaye da sauran halittu a doron qasa, mutane ne da suka yi muguwar rayuwa a zamaninsu da ya wuce don haka ne aka dawo da su waxannan halittu don su xanxana kuxarsu. Saboda haka sai wannan tsari ya taqaita taimakekeniya a tsakanin azuzuwa ya kuma kashe cancanta da qwazo, aka maida su koma-bayan nasaba sai qasar Indiya dake bin wannan tsari sai da ta yi shekara da shekaru cikin talauci da hutanci ba ci gaba. Mahatma Ghandi shi ne ya yi wa wannan tsarin na Indiya *Hindu Caste System* karan-tsaya don haka ne qasar ta samu ci gaba a yanzu. Saboda addinin Hindu ya rarraba al'umma zuwa *q*ananan duniyoyi, kowace duniya ko aji na hamayya da gaba da juna sai tsiraru masu qarfin aji ke samun damar ci gaba. Dubbai kuma na cikin bauta.

Da wannan buri da nufi ne aka kafa makarantar boko a cikin Musulmin Arewa. Domin haka ne taimako da jinqan jama'a ke raguwa ga mutum wanda iliminsa na boko ke qaruwa. Saboda ya shiga cikin wata qaramar duniya wadda daga shi sai 'ya'yansa sai kuma waxanda suke cikin wannan aji ko qaramar duniya. Bugu da qari sai taimakekeniya ta taqaita ainun ga waxanda suke cikin qaramar duniyarsu. Saboda wannan ra'ayi da tunani da fahari da homa sun qeqashe a zuqatan 'yan Boko Musulmi don haka ake kuka da su wajen rowa, son-kai, haxama wajen tara abin duniya da rashin taimako. A yanzu ana yi musu kirari da "Na Gamji ga kuxi ga rowa". Sakamakon wannan tunani ne ilimin boko ya qi faxaxa a Arewa. Don idan aka sauqaqa aka kuma faxaxa ilimin boko don kowa ya samu, yin haka zai rusa tsarin Jajmananci da Arewa ke bi sau da qafa.

Alalmisali, idan Musulmi (mai isasshen ilimin boko) ya ga Almajiri (Sahibul Qur'an) wanda shi ne ke matsayin *untouchable* yana zaune tare da karnuka yana zaman suxin abinci a otel, ana iya zarginsa da zamowa xaya daga cikin waxannan illolin mulkin mallaka huxu:

i. Rashin sanin darajar Alqur'ani

ii. Rashin sanin darajar xan-Adam
iii. Yana fama da ciwon *Sadism*
iv. Yana da halin Hindu.

Domin kuwa babu mutumin da zai ce shi Musulmi ne mahankalci wanda zai kira kansa da wannan suna, sa'an nan ya bar yara almajirai suna gararanba a titi saboda yunwa ta hana su karatun Alqur'ani ya kuma yi biris da wannan halin qasqanci da suka sami kansu a ciki. Abin da Musulmi ke nuna wa duniya shi ne, ga wasu bayin Allah waxanda Alqur'ani ya zama `matsala' a gare su. Saboda babu wani laifi da za'a zarge su da shi in banda son karatun Alqur'ani, da haddace shi da kuma rubuta shi. Saboda wannan son Alqur'ani da Allah (SWT) ya sallaxa a zukatansu ne 'yan'uwansu Musulmi suke gasa masu gurjiya a hannu.

To, Musulmin Arewa za su iya yin iqirarin sanin darajar Alqur'ani saboda ana sa karatunsa a gidajen rediyo ana kuma sa shi a kaset-kaset mutane na saurare. Ai wannan abin da ya nuna shi ne amfani da Alqur'ani ne amma ba bashi daraja ba. Daraja Alqur'ani shi ne kulawa da daraja *Ashabul Qur'an* fiye da wanda ba *Ashabul Qur'ani* ba. A fifita makarantun Alqur'an fiye da kowace makaranta. A daraja Alaramma fiye da kowane mutum. Sa'an nan a daraja *Ashabul Ilm* wato shahararrun malaman nan dake koyarwa a zaure. A kuma ba su daraja da haqqinsu kamar yadda ya kamata, ba tare da sun rayu a kan *Sabil* ba.

A halin gaskiya masu ilimin Addinin Musulunci daga Alarammomi dake cikin Tsangyu a Arewa da mashahuran maluman dake Zaure su bayi ne a qasarsu ta haihuwa. Amfani ake da su ana kuma bautarda su ba tare da an fahimci haka ake yi ba. Duk ilimin Alarammomi da shaihunan malamai da sadaka suke rayuwa tun daga farkon neman ilimi har zuwa lokacin da suka zama shaihunnai. Saboda ba su da albashi daga hukuma domin ilimin Addinin Musulunci ga Gwamnati ba shi da muhimmanci. Don haka waxannan bayin Allah komai girmansu da *Sabil* suke rayuwa. Da yawa daga cikinsu kuma da 'feeding bottle' ake shayar da su, da sunan taimakon addini.

Babu inda ake tozarta mai ilimi kamar Arewa. Roqo ko Bara a farkon rayuwarsa ta karya masa irli. Saboda haka sai ya taso da jin gazawa a rayuwarsa. A sabili da haka ba shi da katavus a harkar rayuwa a matsayin da ya samu kansa a ciki na bauta. Abin takaici ma da bazar waxannan malamai ne ake rawa, amma ba su samun komai sai dai a riqa amfani da su lokaci-lokaci ana basu ahu-ahu! Mulkin mallaka ne ya yiwa Arewa juyin waina. Abin da ya ci malamai da

makarantun Allo shi ya ci Sarakuna. Saboda haka lokaci ya yi da kowane mai ilimi zai ci amfanin iliminsa a duniya da lahira. Zamani ba zai tafi da Arewa ba matuqar masu muhimman ilimi suna cikin qunci da tashin hankali, ba domin komai ba sai don matsayin su ba shi da daraja a qasarsu ta haihuwa. Yana daga daraja Alqur'ani a biya Alarammomi albashi ko da ba sa yi wani aiki sai karatun Alqur'ani. Don kuwa ta haka ne ake adana Alqur'ani a cikin Kwamfiutar dake qirjin Alaramma. Adana Alqur'ani ta wannan haya wato *Document Security* wajibi ne ga al'ummar Musulmi.

A na yi wa Musulmin Arewa dariya saboda ganin yadda dubban almajirai ke yawon bara. Amma suna bara ne a matsayin 'fursinoni' a Arewa waxanda tun daga zamanin Gwamna Lugga wanda gwamnatinsa ta hana su haqqinsu har ya zuwa yanzu. Ana tsammani idan Turawan mulki suka tafi waxannan miliyoyin Almajirai za su sami sa'ida, amma abin takaici sai matsayinsu ya qara tavarvarewa a hannun 'yan uwansu Musulmi. Waxanda suke so su gan su cikin muguwar kama suna bi gida da bola suna tsintar abinci. Waxannan Almajirai sun gane cewa idan suna yawon bara suna cewa, "Allazi Wahidun!, Allazi Wahidun!! Basu samun komai. Amma idan suna waqa suna cewa:

Iya ko xan dago – dago
Iya ko xan qanzo!
Iya ko sauran na jiya ne,
A baiwa almajiri sadaka!

Kafin ya gama baitocin waqarsa sai a kira shi a ba shi sauran abincin da 'ya'yansu suka ci suka rage, waxanda za a baiwa agwagi ko karnuka. Wani lokaci ma irin abincin da ake ba su ko *Bingo* (irin karen Turawa) bai sun-suna shi ballanta ya ci. Irin wannan hali da *Ashabul Qur'ani* suka sami kansu na qasqanci alama ce babba dake nuna matsayinsu a Arewa na *Untouchables*. Bugu da qari kuma akasarin 'yan Arewa suna fama da ciwon *Sadism* (wani nau'in cutar hauka ne dake sa mutum jin daxi idan ya ga xan'uwansa cikin aquba ko masifa). Idan mutum ba sadist ba ne ya kuma san darajar xan-Adam ba yadda zai yarda da halin qunci da *Ashabul Qur'ani* suka sami kansu a qasarsu ta haihuwa. Yaushe kuma son Alqur'ani ya zama matsala ga xan-Adam? Ba talauci ne ya sa jama'ar Arewa son Makarantar Allo ba, Allah ne Ya maida Arewa dausayin Alqur'ani Mai girma.

Idan Musulmi mai halin Hindu ya dubi *Ashabul Qur'an* cikin wahala matsananciya sai ya ji daxi ya kuma riya a zuciyarsa cewa, wannan Addininmu guda da shi, qabilarmu guda da shi haka kuma garinmu xaya da shi. Amma mun banbanta a qananan duniyoyi da muke ciki. Ni ina cikin aji mafi girma da daraja. Sai ya yi hamdala ya ba shi sadakar qwandala ya zaburi motarsa mai tsada 'yar lagwada!

Amma shi ne ya tozarta ba *Ashahubul Qur'an* ba, wanda al'ummarsa ke zaluntarsa take kuma cin haqqinsa kamar karas. Saboda haka idan mutum ya yi tunani mai kyau zai fahimci wannan nazariya sosai. Ilimin boko a cikin Musulmin Arewa na cunkusa wa mutum halin Hindu. Wannan ilimi na qaruwa, tausayi da son taimakon al'umma na raguwa.

Nazariya ta biyu bata da wuyan fahimta. Al'ummar Musulmi a Arewa an kasaftasta ne a bisa tsarin *Hindu Caste System*. Alhaji (Dr.) Abubakar Imam abin da ya faxa wa Gwamna Lugga ke nan, a lokacin da ya je Ingila, Saboda haka ne talauci ya yi wa Arewa katutu ta kuma kasa ci gaba. Don ta kasa sauyawa da zamani.

Shi irin wannan tsari ya bambanta da tsarin Jari Hujja wato *Capitalism* wanda shi yana baiwa kowa dama da iko dai-dai gwargwado. Tsari ne dake buqatar qwazo da aiki tuquru don a sami samu. Yana kuma son dacewa da cancanta. A wannan tsari idan talaka ya nuna qwazo da aiki tuquru zai girma ya zama qasaitaccen attajiri. Idan jahili ya duqufa ya nuna qwazo da aiki tuquru sai ya zama mashahurin Farfesa. Saboda haka tsari ne dake zaburar da jama'a don kowa ya ci da guminsa. Amma a tsarin Hindu wanda Arewa ke bi, qwazo da aiki tuquru su kan zama matsala ga mutum saboda tsari ne da ba ya son dacewa da cancanta. Idan kai ba xan wane ba ne to da wuya ka zama wane! Duk da cewa an san xan wane ba ya zama wane sai ya yi hali da aiki irin na wane.

Allo Xaukakar Arewa

Idan aka dubi halin tavarvarewar da Arewa ke ciki a yanzu, za a ga ai albasa ba tai halin ruwa ba. Saboda wannan al'umma ce dake da tarihin Daular Usumaniyya, ta kuma shahara a duniya. Amma a yanzu jama'arta ta kasa ciyar da kanta saboda tsagwaron talauci wanda qwanji da lalaci suka haddasa mata. 'Yan Arewa mutane ne masu ban mamaki, suna iya sauya wannan mummunan matsayin da suka jefa kansu ciki, in sun sauya halayensu. A yanzu babu wani dalili da zai sanya Almajiri bara don akwai isassun kuxin da za a raya a kuma

kyautata makarantun Allo da xalibansu a Arewa. Amma idan Gwamnati ta tsaya kai da fata cewa waxannan makarantun ba su da muhimmanci kamar gwamnatin Gwamna Lugga, to, ya zama wajibi Qananan Hukumomi su aza wa Musulmi Harajin Allo, don samarda isassun kuxaxe wajen tafiyar da waxannan Makarantu waxanda sune ruhin Arewa! Allah ba Ya tare gaba, Ya tare baya!!

A koyaushe Firimiya Sir Ahmadu Bello katafaren xan Siyasa kuma Basarake, alfahari yake da makarantun Allo ba kyama'rsu ba. A kullum ya kan ce qirqiro su muka yi ba a koyo su muka yi ba. Duk wanda ya san tarihin waxannan makarantu da kuma ayyukan malaman qasar Hausa na farko, babu shakka zai kasance mai so da alfahari da waxannan makarantu. Malam Ahmad Muhammad Sunusi Gumbi, wani malami a Kaduna ya haskaka mana Ayyukan Malaman qasar Hausa, tun daga lokacin da Addinin Musulunci ya shigo wannan qasa tamu Nijeriya a kusan qarni na farko wato cikin shekara ta 55 a Zamanin Daular *Bani Umayya*.[1]

Daga cikin manyan ayyukan da waxannan malamai suka yi haxa da: kafa Addinin Musulunci ta yadda ya zauna da gindinsa ya yi kuma kyakkyawan tasiri ga wannan qasa. Sa'an nan kuma suka qirqiro da hanyar rubutu da karatu na Ajami wanda ya taimaka gaya wajen fahimtar Addinin Musulunci da wayewar kan xan-Adam ta fuskar siyasa da kasuwanci, a wani lokaci mai tsananin wuya. Ayyukansu ne ya xora Arewa a kan gaban sauran al'ummomin Afirka ta Yamma. A wajen bayyana waxannan ayyuka ne Malam A.M. Sunusi Gumbi ya ce:

"Domin rubuce-rubucen da muka fara kaiwa gare su, sun bayyana ne bayan su Malam Abdur-Rahman da Malam Ali waxanda suka yi qoqari wajen fassara haruffan Larabci zuwa Hausa kamar haka: "*Kafun*" su kira shi "*Kaulasan*", 'Mimun, su kira shi 'Min', sa'an nan kuma 'Ha'un' su kira shi 'Hasave'. To, wannan shi ne farkon aikin da malamai na Hausa suka yi a bayan sun koyi harshen Larabci kuma suka yi tsaye wajen nema wa kowane harafi ma'ana cikin harshen Hausa."[2]

Wannan katafaren aikin nema wa kowane harafi na Larabci ma'ana cikin harshen Hausa an yi shi ne a lokacin da babu hanyoyin sadarwa masu sauqi.

---

1 A.M. Sunusi Gumbi, Tarihin Ayyuka Malam Kasar Hausa, Littafi na farko, Gumbi Enterprises Ltd., Kaduna (1988) shafi na 1.

2 *Ibid*, p. 2

Malaman sun nemi karatu cikin wahala sun same shi a cikin wahala saboda haka sai suka nemi hanyar da za su sauqaqa shi don al'ummarsu ta same shi cikin sauqi kuma wadatacce. A wannan lokaci babu haxarin da ya fi tafiya tsakanin wannan qauye zuwa wancan ko tsakanin wannan gari da wancan dake nesa da shi saboda a qasa ake tafiya tinkis-tinkis ko kuma bisa raquma ko jakuna in da hali. A wannan lokaci za ka ga malamai alarammomi rataye da Qur'ani a cikin gafaka da almajiransu xauke da alluna cikin jerin gwano suna tafiya tinkis-tinkis tsakanin wannan Tsangaya zuwa waccan kuma tafiya mai nisan gaske.

Akwai haxura masu yawan gaske da waxannan matafiya ke fuskanta. A lokacin da malam Abdur-Rahman da malam Ali suka shigo qasar Hausa babu wani ci gaba wanda ya wuce na wannan qarnin, jama'a na fama da masifar yunwa saboda yaqe-yaqe a tsakanin su. Sa'an nan ga farmakin namun jeji iri-iri da kuma barqewar annobar cutututuka daban-daban. Dubbai na mutuwa a kowane lokaci saboda waxannan masifu iri-iri dake addabar al'ummar wannan zamani. Jama'a kuma ba su sakewa saboda farmakin yaqe-yaqe tsakaninsu ko kuma daga maqwabtansu. Idan kuma dare ya yi babu fitilu sai aci-bal-bal ko wutar kara ake amfani da su wajen karatu ko hira.

A cikin waxannan matsatoli masu haxari malaman qasar Hausa suka yi wani irin katafaren aiki kuma gagara-koyo suka qirqiro da Rubutun Ajami. Nasara da tasirin wannan aiki ne ya bunqasa harsnen Hausa har ya watsu a kusan duk faxin nahiyar Afirka baki xaya. Waxannan mashahuran malamai bayan sun sami ilimin Addinin Musulunci cikin harshen Larabci mai wuyan gaske sai suka haxu suka qirqiro hanyar rubutun Ajami domin su sauqaqa wa jama'arsu sani da fahimtar Addinin Musulunci. Har ila yau nasara wannan aiki ya nuna akwai kyakkyawan haxin kan malaman qasar Hausa. Don kuwa sun karvi duk haruffan Larabci da aka baiwa ma'ana cikin harshen Hausa. Don kuwa duk qasashen *Kaulasan* ake kiransa. Saboda haka abin al'ajabi ne yadda duk waxannan qasashe suka daidaita a kan fassara guda, a lokacin da babu hanyar sadarwa mai sauqi. A wannan lokaci da talauci ya yi wa mutane katutu ba su nemi kuxi ba wajen bada karatu sai dai inda sadaka ta samu.

Har ila yau nasarar wannan qasaitaccen aiki ya nuna jama'ar kasar Hausa na da kaifin basirar xaukar wannan aiki da kuma yadda suka lugwigwita Larabci ya kuma zama kamar harshen Hausa, waxanda ya taimake su fahimtar Addinin Musulunci har suka yi fice a duniya tun a wancan zamani. Bincike ya nuna waxannan malamai Hausawa ne. Domin kuwa a wancan zamani babu qabilar da

ta fi su yawo qasashe-qasashe. Bayan da suka sami karatu mai zurfi a Jami'ar Kirawan ta Tunisiya da Askandariya ta qasar Masar da sauran qasashe, sai suka komo qasar Hausa inda suka yi wannan muhimmin aiki, gagara koyo. Domin ko a yanzu duk da ci gaba wajen ayyukan ilimi da sadarwa da muke da shi, ba za mu iya qirqiro kamarsa ba. Don kuwa waxannan mashahuran malaman ba su tsaya a qirkiro hanyar Rubutun Ajami ba sai da suka kammala ayyukansu da sauqaqa fassarar Larabci zuwa Hausa. A wannan vangaren kuma sai Malam Sunusi Gumbi ya ce suna fassara Larabci zuwa harshen Hausa kamar haka:

"Idan an rubuta da Larabci an ce 'La-Yahillu', to, sai waxannan su fassara wa almajiransu cikin harshen Hausa kamar haka: 'Ba ya halatta: Da haka ne suka yi ta koya wa 'yan Arewacin Nijeriya ilimin Addinin Musulunci da luggar Larabci ta hanya mafi sauqi, wanda hakan ya sa al'ummar Hausa ta karvi Addinin Musulunci, har ta kasance kamar ta Hausa ne aka aiko Annabin da ya zo da Addinin Musulunci ga mutanen Afirka ta Yamma, domin Kano da Katsina a qarshen qarnin nan na shida sai suka zama wasu manyan birane da mutanen Afirka ta Yamma ke zuwa neman ilimin Addinin Musulunci bayan da can suna zuwa kasuwanci. Kuma wannan ya sanya baqaqen fata na Afirka ta Yamma, wato Fulani da Zabarmawa da Buzaye da Yarabawa duk suna zuwa waxannan garuruwa suna koyon Hausa domin su koyi Addinin Musulunci, kuma sukan yi zaman Koyon Hausa a wajen malaman Hausa sa'an nan su koyi Addinin Musulunci da luggar Larabci ta hannun waxannan malaman, kamar dai yadda mutanen Bulgeriya ke yi wa almajirai masu zuwa can neman ilmi a yanzu."[1]

Waxannan malamai sun yi aiki wajen yaxa Addinin Musulunci da kuma gina harshen Hausa da qulla zumunta tsakaninsu da 'yan'uwansu dake Afirka ta Yamma, wanda ya ke har yanzu da wannan aikin nasu muke abokantaka da 'yan'uwanmu na Afirka ta Yamma, ko da yake dai Mulkin Mallaka ya yi irin nasa varnar wajen rage wannan zumunta tamu. Duk waxannan muhimman ayyuka an yi su ne a Tsangayun makarantun Allo. Idan malami ya sami ilimin Alqur'an mai girma a Tsangaya sai ya tafi birni inda zai koyi ilimin Addininsa a wurin malumman Zaure. Saboda haka sai waxannan cibiyoyi suka zama kamar jami'oin samun ilimi a wancan zamani. Waxannan cibiyoyi ne suka horar da da dubban Sarakuna da Alqalai waxanda su ne suka ciyar da Arewa gaba a harkokin mulki,

[1] A.M. Sunusi Gumbi, Tarihin Ayyuka Malam Kasar Hausa, Littafi na farko,shafi 4-5

siyasa da kasuwanci. Waxannan cibiyoyi ne kuma suka xaukaka harshen Hausa fiye da kowane harshe a Afrika. Saboda haka taimakon da Makarantun Allo da na zaure ke bayarwa har yanzu suna da yawan gaske. A dalilin haka ne wannan malami ya ce:

"To, wannan irin aikin da waxannan malamai suka yi ya sa an sami cikakkiyar fahimtar juna tsakanin qabilun Arewa ta hanyar siyasa da addini da kuma tattalin arziki, wannan aikin ya sa wata gagarumar jituwa tsakanin al'ummar Hausa da Larabawa saboda fahimtar juna da ake yi wajen kasuwanci. Wannan shi ne ya sa a lokacin da manyan malamai na qasashen Larabawa suka fara shigowa cikin Arewacin Nijeriya sai suka iske cewa Arewa qasa ce ta malamai, kuma Larabawa ne a harshe amma Hausawa a fatar jikinsu.

Don haka zumunta ta qullu kuma Addinin Musulunci ya bunqasa, kuma aka sami manya-manyan malamai masu rubuce-rubuce cikin harshen Larabci, ko da yake dai ba Larabawa ba ne. Kuma hanya ta buxu cikin sauqi ta qulla zumunta tsakanin 'yan Arewacin Nijeriya da kuma Gabashinta, wato Sudan da Misra. Sai mutanen Nijeriya suka yi ta tafiya aikin hajji ba tare da wata tsangwama ba. Wata babbar nasara da malaman suka yi ita ce an samu wasu manya-manyan Sarakuna daga bisani waxanda suka rungumi Addinin Musulunci tare da aqida mai kyau. Waxannan Sarakunan su ne kamar Sarkin Kano Muhammadu Rumfa. Wannan ya sa Arewacin Nijeirya ta zama kamar dausayin furen 'ya'yan itatuwa a Ingila saboda kyau. Ga dai ilimi, ga kuma wayewar kai, sa'an nan kuma ga iya kasuwanci. Don haka sai Arewacin Nijeirya ta shiga cikin tarihi na qasashen Musulmin duniya, har ma wasu manya-manyan malamai irin su Sheikh Abubakar Maghili ya kawo ziyara domin ya gani da idanunsa bisa ga abubuwan da kunnuwansa suka ji na cewa, qasar Hausa qasa ce ta Larabawa a cikin baqar fata."[1]

Nasara da tasirantuwar ayyukan waxannan malamai ne suka xaukaka qasar Hausa har ta zama wata abar girmamawa shekaru aru-aru kafin Turawa su fara yawon duniya. Tun daga wancan zamani ne aka sami damar qulla zumunci ta huldar kasuwanci da siyasa wanda ya dunqule qasar Hausa da qasashen Ghana, da Borkina-Faso, da Togo da Benin, da Mali da Senegal da Chadi da Kamaru da

[1] A.M. Sunusi Gumbi, Tarihin Ayyuka Malam Kasar Hausa, Littafi na farko, shafi na 5

Nijar. Wannan qasa ta qara danqon zumuncinta da qasashen Sudan, da Libiya, da Tunisiya da Mauritaniya da sauran qasashen Afirka ta Arewa har da na Gabas Ta Tsakiya. Saboda haka sai kyawawan ayyukan waxannan malamai ya zama harsashi mai qarfi da qarko ga zuwan Shehu Mujaddadi da ayyukansa.

Ayyukan malaman Hausa na farko sun taimaka gaya wajen baiwa qasar Hausa damar hulxar Diplomasiya ilimi da kasuwanci da qasashen qetare. A dalilin wannan ci gaban ne yasa Sarkin Katsina Muhammadu Korau ya gayyato mashahurin malamin nan Sheikh Abu Abdullahi Muhammad Abd al Karim Ibn Muhammad al Maghili zuwa birnin Katsina a Kasar Hausa a cikin watan Oktoba 1492. Almaghili ya sami tsawon shekaru biyu a wannan birni inda ya inganta harkokin mulki a wannan masarauta. A dai-dai lokacin da Katsina ke inganta masarautarta da ziyarar Almaghili ne Christopher Columbus ya sauka a Arewacin tsibirin Haiti a ran 12 ga Oktoba 1492, bai ko gano Amurka ba.[1] Daga Katsina sai Almaghili ya tafi Kano.

A lokacin da Almaghili ya ziyarci birnin Kano, har ya taimaka wa Sarkin Kano Muhammadu Rumfa da wasu littattafai: *Taj al Din Fi Ma Yajibu Alal Muluk*i wato Tsarin Mulkin Musulunci da ya Wajaba a Kan Sarakuna da *Mukhtasar Fima Yajuz Alal Hukkam*, wato Taqaitaccen Bayani a Kan Abin da ya Wajaba a Kan Mahukumta (Alqalai). Duk waxannan littattafai sun taimaka wajen havaka sha'anin mulki da alqalanci a Kano har ma da qasar Hausa baki xaya. A qarni na goma sha-shida qasar Hausa ta yi nisa wajen harkokin ilimi da fasaha, a lokacin da qasashen Turai da yawa ba su taso ba. Saboda ayyukan da malaman Makarantun Allo da na Zaure suka yi da subahin fari ne suka kai wannan qasa ga xaukaka. Domin haka ne a lokacin da qasar Hausa ta bunqasa harkokin ilimin da fasaha da mulki da kasuwanci a wannan lokaci ne qasashen Turai suke cikin Duhun Kai wanda a Turance ake kira da *Dark Ages* (1100 – 1500AD). Bugu da qari a lokacin da Shehu Usuman Xanfodiyo ya fara wa'azinsa a shekarar 1774, a wannan lokaci qasar Amurka ba ta sami 'yanci ba sai bayan shekaru biyu. A ran 4 ga Yuli 1776 ne kasar Amurka ta kai ga samun 'yancinta, bayan a wannan shekarar ce Mujaddadi ya dawo daga Xegel a loakcin da yake yawon wa'azinsa.

---

[1] Lawal Musa Xanqwari, *Comparative Reflections; On the Establishment and the Collapse of the Sokoto Caliphate*, (an unpublished article), shafi na 3.

Wa'azin Shehu Mujaddadi ya watsu sosai a lokacin da aka yi zaven shugaban qasar Amurka na farko a 1788 da kuma sake zavensa a 1792.[1]

A lokacin da Yarima Otto Von Bismarck yake kafa qasar Jamus a 1871 – 1890, a wannan lokaci Daular Usumaniyya tad axe da kafuwa hart a sami Sarki na takwas, Sarkin Musulmi Abubakar Xan Atiku Mai Ravah (1873-1877).[2] Saboda haka qasar Jamus ita ba tsarar qasar Hausa ba ce. Duk waxannan ci gaban xan-Adam da aka samu a qasar Hausa sun yiwu ne saboda gudunmawar da Makarantun Allo da malamai da Shaihunan wannan yanki ne suka bayar. Duk al'ummar da ta qirqiro Rubutun Ajami ta kuma nuna ci gaba a harkar ilimi da fasaha da sufuri da kasuwanci kamar yadda qasar Hausa ta yi da asubahin fari, to, ba shakka zata samu maqiya masu yawa a ciki da wajenta. Qasar Ingila ta san tarihin Arewa ciki da waje don haka da ta angije Daular Usumaniyya bata vata lokaci ba wajen tarwatsa Makarantun Allo. Domin sune qashin bayan ci gaban wannan qasa da ta daxe tana buwaya a tarihi.

A farkon qarni na goma sha-takwas Shehu Usuman Xan Fodiyo ya bayyana a qasar Hausa, ya yi jihadin Xaukaka Addinin Musulunci. Ya kuma kafa Daular Usumaniyya wadda ta buxe wani sabon falle a tarihin wannan qasa. Wannan Daula sai ta qara ciyar da qasar Hausa gaba ta hanyar mulkin Sarakuna. A wannan zamani ne malamai suka shiga rubutu da fassara litattafan Addinin Musulunci zuwa harshen Hausa. Waxannan littattafai da aka wallafa kuma waxanda aka fassara sun taimaka gaya wajen raya Addinin Musulunci, da bunqasa siyasa da kasuwanci tare da wayewar kan xan-Adam. Ita ma wannan Daula sai da ta yi suna a idon duniya ta kuma bada gudunmawar ci gaban xan-Adam. Bayan shekara xari sai Turawa suka angije wannan Daula.

A farkon qarni na goma sha-tara ne Turawan Ingila suka shigo Arewa, suka angije Daular Usumaniyya wadda suka kira Mulkin Fulani, sai suka kafa Mulkin Mallaka. Tun kafin su shigo Turawa suna da cikakken tarihinta, qarfin arzikinta da buwayar da ta yi a duniya. Sa'an nan sun san Sarakuna da malaman makarantun Allo ne gadon bayan Arewa. Saboda haka cikin irin wani salon mulki sai suka kawo mulkin *Indirect Rule* wanda ya zaizaye qarfin sarakuna daga qarshe kuma ya dasa aya a mulkinsu. A cikin wannan shiri kuma sai suka tarwatsa

---

1 Lawal Musa Xanqwari, *Comparative Reflections; On the Establishment and the Collapse of the Sokoto Caliphate*, shafi na 7

2 *Ibid*, shafi na 8.

makarantun Allo suka kuma maida dubban malamai da al'majiran dake cikinsu 'Fursinonin Sake' a qasarsu ta haifuwa. A wannan matsayi suke tun daga mulkin mallaka har yanzu. A dalilin wannan mulki ne makarantun Allo da xalibansu *Ashabul Qur'ani* suke cikin qasqanci, talauci da wulaqanci a matsayin da suka sami kansu na Fursunonin Sake. Tun da aka ci qasarsu da yaqi sai gwamnatin Mulkin Mallaka ta zartar da hukuncin cewa ilimin Addinin Musulunci babu ruwan Gwamnati da shi.

A lokacin da wasu Shugabannin hamvararriyar Daular Usumaniyya ta sadu da Gwamna Lugga a Sakkwato ranar Alhamis 20 ga watan Maris, 1903. ga abin da Gwamna Lugga ya ce masu:

"Na yi murna da ganin ku, na yi murna da dawowar ku. Kun yaqe mu, mun ci ku, mun kore ku, yanzu kuma yaqi ya qare sai zaman aminci. Mu ba al'adarmu b ace mu kama waxanda suka yaqe mu, ko mu kashae su. Saboda haka duk waxanda suka gudu su dawo gidajensu su nyi zamansu.

"Ba za a sa baki cikin addininku, ko kuma kan Sarkin Musulmi, da yake shi ne shugaban addinin naku. Gwamnatin Ingila ba ta tava karambanin sa kanta kan wani addini ba, ko haraji ko hanyar hukunci irin na hana laifuffuka wanda yake maganar gwamnati ne, ban da kuwa addini.[1]

A wannan rana ce Gwamna Lugga ya sa aka fassara wa su Waziri, da Galadima da Sarkin Gobir Umaru, da Marafa Maiturare, da Sarkin Burmi da Sarkin Zamfara da Sarkin Kabi tsari da dokokin Mulkin Mallaka dake tafe. Ko da yake an yaqi Turawa amma sun ci Arewa da yaqi. Saboda haka a zo a yi zaman aminci. To wane irin zama ne za a yi, sai Gwamna ya gabatar da dokoki mafiya illa a cikinsu su ne: "Ba za a sa baki ba cikin addininku." Saboda Gwamnatin Ingila ba ta katsalandan a harkar addini. Abin da ake nufi shi ne ba ruwan Gwamnati da addini, ba kuma za a tilasta jama'a bin wani addini ba. Watau malamai da Makarantun Allo ba ruwan Gwamnati da su. Saboda haka su tafi a matsayinsu na Fursunonin Sake. Dubban Makarantun Allo da Almajiransu Gwamnati b ata san da zamansu ba, ilimin da suke bayarwa kuma ba shi da wani muhimmanci a wannan sabon tsarin mulki da Ingila ke wa jagoranci.

To, amma kuma "… ko haraji, ko hanyar hukunci irin na hana Laifuffuka, waxanda yake maganar Gwamnati ne, ban da kuwa addini." Wannan doka ce mafi

[1] Abdulmalik Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya Ta Arewa*, shafi na 124

muni saboda ita c eta kashe shari'ar da Turawa suka kawo. Duk waxannan dokoki sun raunana Addinin Musulunci.

Dokar farko ta wofintar da malamai da iliminsu. Doka ta biyu kuma ta yi wa shari'a karantsaye. Ita kuma wannan dokar sai ta raba ibada da addini. Gwamnatin Ingila ta bai wa malamai su gina ibada amma b ata huwace musu gina addini ba. Ayyuka kamar koyar da salla, da azumi da aikin Hajji Fursunonin Sake na da izinin koyar da su yadda addininsu ya tanada. Amma duk ayyukan da suka shafi rayuwa ta duniya kama hanyar mulki da hukunci, shari'a ne na Gwamnati. Saboda haka ba ruwan malamai da su.

Saboda haka sai illar doka ta biyu ta yi bakin damo, ta kashe Shari'a ta kuma raba addini da Siyasa. Tun daga wancan zamani har ya zuwa yanzu Musulmin Arewa sun kasa magance waxannan illoli. Rayuwar Musulmi ba ta kamala ba sai tana bin hukuncin Shari'a. sa'an nan kuma Musulunci ba ibada ba ne, domin duk abin da za a yi hisabi a kansa addini ne. saboda haka rayuwar Musulmi baki xayanta sai ta zama ibada. A dalilin haka ne Addinin da Siyasa 'yan tagwaye ne a haxe wato *Siamese Twins* ba a raba su. In kuma aka raba su sai a rasa su.

Domin waxannan illoli su yi tasiri a kan Musulmi sai gwamnatin Lugga ta wofintar da malamai da Makarantun Allot a kuma maida ilimin Addinin Musulunci mara muhimmanci saboda ba ruwan Gwamnati da shi. Sa'an nan kuma ta karkata hankalin malamai wajen gina ibada ba addini ba. An haramta haxa ibada da mu'amala. Aikin Malamai bai wuce koyar da salla, da azumi da aikin hajji ba amma kuma ba shi da albashi, domin ba ruwan Gwamnati da shi da iliminsa da Makarantar Allo don kuwa matsayin malamai na Fursunonin Sake ne a qasarsu a kuma hannun Musulmi.

KASHI NA SHIDA

Arewa a Yaqin Duniya

Sojojin Afirka ta Yamma

Waxannan sojoji wato sojojin 'WAFF' wato *West African Frontier Force*, da aka kafa ta a cikin shekarar 1877 saboda ta kare daulolin Ingila da ke Yammacin Nahiyar Afirka. Wannan ya zama dole saboda farmakin da Faransawa suka yi wa Borgu, don haka sai Ingila ta lura da cewa ya kamata ta haxa sojojin da za su kare bakin iyakokin daularta. Wannan shi ne maqasudin tanadin waxannan sojoji. An kuma kwashi 'yan Yammacin Afirka da dama cikin wannan rundunar soji waxanda galibinsu suna zaune ne a gavar teku.

Rundunar sojojin na da qarfin soja da suka yi yawan askarawa dubu biyar da xari bakwai da tamanin da uku (5,783), a cikinsu 'yan Afirka sun kai yawan dubu biyar da xari huxu da goma sha-bakwai (5,417), sauran kuma Turawan Ingilishi ne. Akwai Ofisoshin Ingilishi 174 (British Officers), da N.C.O. 192 (British NCO). Akwai kuma karabiti masu yawan 4,977. Ita wannan runduna na da Bataliyar mayaqan qasa (Infantry Battalion) guda biyu da Bataliyar 'yan Igwa wato 'yan Atilari. Rundunar sojojin 'WAFF' suna qarqashin Birgediya-Janar Cunliff.

An kafa rukunin sojoji a garin Jebba a cikin shekarar 1901. A cikin wannan shekara an kwashi wani kamfani cikin hanzari domin zuwa garin Zariya, saboda roqon da Sarkin Zazzau Kwasau ya nema ga Gwamna Lugga da ya taimake shi da sojoji. Ko da yake an kwashi sojoji zuwa Birnin Zazzau amma ba su yi yaqi ba. Sun tafi Zariya ne saboda Sarkin Kwantagora zai farwa Sarki Kwasau da yaqi amma qura ta lafa kafin sojojin su isa Zariya. A can Zariya aka bar su har cikin shekarar 1913.

A ranar 21 ga watan Fabrairu na shekarar 1913 aka kwaso rundunar sojojin WAFF zuwa Kaduna, inda aka yi masu masauki a Barnawa kafin a gama gina barikinsu a cikin Kaduna.

A cikin Turawan mulki sai aka mayar da xari da goma sha-tara (119) aikin soja. A cikin garin Kaduna an kwashi leburori dubu biyar wajen aikin soja, wannan har ya kawo wata 'yar cikas wajen ci gaba da tafiyar da ginin sabuwar Hedkwatar. Varkewar yaqin Gabashin Afirka *East Africa* shi ma ya daxa qara wa mazaje qaimi, wajen shiga aikin soja.

Wajen rundunar sojojin WAFF da ke kafe a Kaduna wadda aka tanada don vacin rana irin ta wannan lokaci, su masun sami qarin sojoji kurata. An samu qarin kurata xari biyu da biyar (205) daga ciki da yaqin Gabashin Afirka ya varke. An qara samun qarin kurata tamanin da takwas (88) a cikin wannan rundunar. An

kuma qara samun kurata xari shida da arba'in da huxu don shirin yaqin *East Afirka*.

Dubban sojoji kurata da aka kwasa, sai aka buxe masu buzaye wato wajen koyon harbi a wurare da dama a garin Kaduna. Waxanda suka samu isasshen horo kuwa sai a tura su fagen fama, inda suka je suka nuna bajintar bai wa kura nama. Yaqin Duniya na xaya ya barke ne a shekarar 1914. An kuma sami shekaru huxu ana gwabza wannan yaqi. A dalilin barkewar wannan yaqi ne zai qasar Ingila ta nemi taimako daga qasashen da Ingila take reno.

Asusun Taimakon Yaqi

Da yaqin duniya na xaya ya varke, sai Gwamna Lugga ya buxe asusun neman taimakon yaqi wato *War Treasury Fund* da na qungiyar masu agaji wato *Red Cross Society*. Sarakunan qasar Hausa sun taimaka gaya wajen mara wa Turawa baya, ba dakaru ba kawai har da zunzurutun kuxi. An raba karvar taimako kashi biyu: kashin farko hukumar lardi ke bayarwa asusun yaqi taimako. Kashi na biyu kuma na jama'ar gari ne tare da Turawa, su kuma mai taro mai sisi an buqaci su taimaka wa qungiyar Agaji wato *Red Cross Society*.

Sarkin Zazzau Malam Aliyu Xan Sidi ne ya fara buxe fili da bayar da taimakon kuxi da sawun takalma qafa xari biyar (500) domin sojoji kurata a farkon varkewar yaqin. Ga kuxaxen da Hukumar Zariya da jama'arta suka agaza wa asusun yaqi da qungiyar 'yan Agaji:

Shekara	Asusun Yaqi	Qungiyar Agaji
1914	£1,750.00	-
1915	£3,000.00	£175.00
1916	£4,000.00	£753.00
1917	£2,000.00	£396.00
1918	£500.00	£711.00 [1]

Cikin shekaru biyar da aka yi ana gwabza wannan yaqi, asusun taimakon yaqi ya samu zunzurutun kuxi har fam dubu goma sha-xaya da xari biyu da hamsin (£11,250) daga hukumar Zariya, sa'an nan jama'ar gari sun ba da taimakon fam dubu biyu da talatin da biyar (£2,035). Waxannan kuxaxe maqudan gaske ne a wannan lokaci.

Saboda samun isassun kuxi da dakarun yaqi da Turawan mulki suka samu, yana xaya daga cikin dalilan da ya sa Ingilishi suka samu galabar wannan yaqi. Lallai! 'yan Arewa da Sarakunansu sun ci a yaba masu sosai. Allah Ya azurta

[1] An samo daga Zariya Provincial Gazette.

Arewacin Nijeriya da arziqin qasa da na jama'a. Mun ji kaxan daga cikin albarkacin qasa da Turawa suka ci. Yanzu kuma sai mu ga yadda Turawan Ingilishi suka ci arziqin Arewa na jama'a. Varkewar yaqin duniya na xaya wanda aka fi sani da yaqin Kamaru da na *East Africa* shi ya ba su damar cin wannan albarka.

A ran 4 ga Agustan shekarar 1914, wannan yaqi ya varke. A wannan lokaci Nijeriya na da wata takwas da kafuwa Haxaxxiyar Qasa. Saboda ran xaya ga Janairu shekarar 1914, aka haxa Kudu da Arewa suka zama gwamnati xaya, a *qarqashin* Gwamna guda a Ikko. Gwamna Lugga, shi ne ya zama gwamnan farko na Haxaxxiyar Nijeriya. Kafin Nijeriya ta cika shekara xaya, sai ga yaqin Kamaru ya varke wato Yakin duniya na Daya.

A Gabashin Nijeriya akwai makekiyar qasar Jamus da ake kira Kamaru. Nijeriya na cikin haxari, don Jamus a wannan yaqi ita ce babbar abokiyar gabar Ingila. Saboda haka sai soJan Ragamar Nijeriya tare da taimakon Faransawa da Beljinawa (mutanen Belgium) suka afkawa Kamaru da yaqi. A dalilin haka sai aka nemi qarin sojoji.

Saboda varkewar yaqin Kamaru da na *East Africa*, sai aka buxe shiga aikin soja, aka kuma rugungunta horar da sudon su tafi su yi maganin farmakin Jamusawa da ya vullo a Kamaru daular Ingilishi. Ko'ina a cikin qasashen Arewa sai mazaje ke shiga aikin soja, jim kaxan an kwashi dubban 'yan Arewa aikin soja.

Yaqin Kamaru da *East Africa*

Yaqin Kamaru ya varke a cikin watan Agusta na shekarar 1914. Abin da ya sa ake kiransa yaqin Kamaru, saboda lokacin da yaqin ya tashi, manya-manyan qasashen Turai irin su Jamus da Faransa da Ingila suna da dauloli masu yawa a Afirka, don haka kowanne daga cikinsu ya yi qoqarin hana xayan shiga daular sa. A nan qasar sai Turawa suka xebi dubban 'yan Nijeriya suka kai su Kamaru ta Kudu don hana Jamusawa cin galaba. An yi shekara xaya da rabi ana yi wa wannan qasa luguden wuta kafin aci ta da yaqi. Bayan wannan yaqi sai Majalisar Xinkin duniya ta rabawa Faransi da Ingila wannan qasa kamar kashi xaya cikin shida aka haxa da Nijeriya, amma ba qasar Nijeriya ba cewato qasar amana ce.Yankin Kudu shi aka mayar lardin Kamaru, yankin Arewa kuma aka haxa da qasar Adamawa da Barno.[1]

Bayan yaqin Kamaru sai aka tura soJan Ragamar Nijeriya zuwa Afirka ta Gabas *East Africa* don su taimaka wajen qwato wata makekiyar qasar Jamus da ake kira Tangayika. Kamar sojoji dubu shida (6,000) da 'yan xaukar kaya dubu huxu (4,000) aka tura wajen wannan yaqi. Niven ya ce, "waxannan sojoji sun sha wahala sun kuma yi asarar mutanen su da yawa, amma sun nuna jarumtaka ta

[1] CR Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na 101

innanaha! " Akasarin waxannan sojoji 'yan Arewa ne. Niven ya qara da cewa, "sun nuna gayar jarumtaka. " Sun komo Nijeriya cikin watan Maris 1918. Yaqin kuma ya qare ran sha xaya ga Nuwamban shekarar 1918. A wannan yaqi kuwa an ci Jamus da abokanta.

Ko da yaqi ya qare sai aka bar wa Ingilishi mulkin Kamaru, su kuma suka haxa ta da Nijeriya suna mulkinsu baki xaya. Idan batu na nuna Jarumtaka ne to, a nan 'yan Arewa ke yin fice. Don Jarumtakar su har Sarkin Ingila ya ba da izini a kira sojojin WAFF da suna *Royal West African Frontier Force* (RWAFF).[1]

An gama yaqin duniya na farko a cikin shekarar 1918, wannan ya sa an sallami sojoji da yawa. Amma varkewar Yaqin Duniyar na biyu a cikin shekarar 1939, ya dawo da kwasar sabbin sojoji domin a horar da su. Idan batu na yaqi ne, to, 'yan Arewa ne aka sani, kuma su aka fi buqata ba domin komai ba sai don qwarewarsu wajen bai wa kura nama.

An kwashi dubban 'yan Arewa zuwa yaqin duniya na Xaya, abin da ya kamata sai mu bi su mu ji yadda suka fitar da qasarsu daga jin kunya. Su waxannan bayin Allah su ne rukunin farko na 'yan qasa da suka fara fitar da sunan qarsarsu a idon duniya, ba don komai ba sai don tsagwaron jaruntakar da suka nuna a wannan yaqin.

Ko da yake Turawa sun shigo Arewa, sun ci 'yan Arewa da yaqi kafin su kafa Mulkin Mallaka amma ba su tafi ba sai da aka nuna masu jaruntakar mutanen Arewa. Shi kansa Gwamna Lugga ya tsinke da bajintar 'yan Arewa a wannan gagarumin yaqi. Su ne ake wa kirari da Hausawan Ikko don jarunta.

Kafin yaqin duniya na xaya Turawa sun kafa Mulkin Mallaka, sun kuma nuna qasaitaccen iko a wannan makekiyar qasa. A wannan lokaci idan 'yan Arewa suka ga Tarawa sai su natsu suna masu girmamasu suna kaffa-kaffa da su don tsoron kada su musguna masu. A wannan lokaci Nasara, 'Zaki' ake ce masa. Abubuwan da suka sa Nasara samun wannan daraja shi ne cin Arewa da yaqi da suka yi sannan da kayayyaki na ci gaban jama'a da suka kawo da kuma dabarar yin abubuwa.

Maqasudin da ya sa Turawa suka samu galaba bisa 'yan Arewa suna da yawa, amma mafi girma shi ne rashin haxin kan qasashen Hausa a wannan lokaci da kuma kayayyakin yaqi da Turawa suka yi amfani da su kamar bindiga da Igwa. Waxannan dalilai sun karya 'yan Arewa sannan aka samu galabar su. Babu batun tsoro ko rashin nuna jaruntaka a cikin wannan al'amari saboda bai yiwuwa a gwada jaruntar mai yaqi da kibiya da mashi da takubba da jaruntar mai yaqi da bindiga da Igwa. Idan ana son a gwada bajinta ne, to, sai kowanne ya yi amfani da makami iri xaya. Ta nan ne za a samu jarumai a kuma sansu.

---

[1] CR Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na 101

Yaqin Duniya na xaya ya ba da wannan jarabawar, domin Turawa da 'yan Arewa sun yi amfani da makamai iri guda da dabarun yaqi iri guda. Sannan kuma sun haxu sun yaqi magabci guda wato Jamusawa. A wannan yaqi ne Turawa suka tsinke da jaruntakar 'yan Arewa ta inna-naha!

Tun da yaqi yana xaya daga cikin dalilan da Turawa suka sami kwarjini bayan sun ci Arewa, to, sai ga shi Allah Ya kawo wani yaqi wanda ya bai wa 'yan Arewa kwarjini. Mazauna garin Kaduna sun ga abin mamaki, abin da ko a mafarki ba su tava tsammani za su gani ba, a lokacin da sojoji suka dawo daga yaqin duniya na Xaya.

A wannan lokaci ne sai ga Turawa sun taho da 'yan Arewa suna kuma kaffa-kaffa da su ba domin komai ba sai don bajintar su a fagen fama. Dawowar sojojin ya qara bunqasa garin Kaduna da jama'a. Jaruman yaqin duniya na farko, sai jama'a suka ga ba sa raga wa Turawan mulki ko kaxan. Mutanen da ake wa "Ranka ya daxe zaki " sai ga shi, su ake yi wa tsawa ake kuma kiran su 'Birai'. A wannan lokaci sai Turawa suka natsu suka sha jinin jikinsu sannan suka rage homa da girman kai.

Allah Sarki duniya! Dalilin da ya sa Turawa ganin wannan tasku shi ne, saboda sojojin da suka tafi Kamaru sun ga Turawa ba su nuna jaruntaka ba. Wajen yaqi da Jamusawa, sai aka fahimci ba su da katavus. To, don Allah fankamar me raggo zai yi wa jarumi?

Tsofaffin sojojin yaqin duniya na Xaya, waxanda Turawa suka zo da su suna taka tsantsan da su, an bai wa da yawa daga cikinsu muqami a garin Kaduna. Ko da yake wasunsu an yi masu rauni amma sun taimaka wajen tafiyar da al 'amarin Kaduna. Jaruntakar waxannan bayin Allah ta kawo wa Arewa fa'idodi da yawa.

Mafi daraja, su ne na farko dai sun sama wa Nijeriya kwarjini a idanun duniya, na biyu kuma shi ne qarin so da qauna da 'yan Arewa suka samu a idanun Turawan mulki. Wannan abu haka yake don babu wanda zai manta da wanda ya fitar da shi kunya. Saboda jaruntakar 'yan Arewa ne ya sanya Turawa suke nuna masu fifiko, wanda a yanzu wasu kan cewai wajen aikin soja Turawa sun fi son 'yan Arewa. Wannan batu haka yake domin kuwa inda ake samun ruwa isasshe, sai a kai ma'aikatar ruwa wajen, haka kuma inda ake samun kayan ma'adinai sai a yi hanyoyi zuwa wajen. To, inda ake samun jarumai fa? A wannan waje, sai a buxe manyan makarantun horar da sojoji Bataliyoyin soji, da makarantunsu da ke Arewa, an tanade sune ba domin komai ba sai don shirin vacin rana.

Abin nufi a nan shi ne manya-manyan makarantun sojoji da Bataliyoyin sojoji da suke Arewa, an same su ne ba don su 'yan Arewa sun fi 'yan Kudu faxin qasa ba ne, a'a don sun fi su jaruntakar yaqi ne. Albarkacin jaruntakar mazan-jiya shi ne kuma 'yan mazan-yau ke ci, shi kuma mazajen za su ci a gobe.

Ko da yake wannan xan littafi ba zai xauke duk labarun dakarun yaqin ba, wasu kuma ba a san garinsu ba. Amma kaxan daga cikin jarumawan da aka zo da

su Kaduna akwai kamar su Keftin Na Kauru da Keftin Manu Zariya da Mai Damisa da Bukar Mandara da Garba Tasawa da sauransu. Kusan kowannensu sai da ya riqe muqami a garin Kaduna. Saboda jaruntar 'yan Arewa a wannan yaqi ne shugaban Rundunar Sojan WAFF da wasu Janar-Janar suka kawo ziyarar bangirma ga Sarakunan Arewa.

Sir A. Wood Rentorn wanda shi ne Kwamishinan Yaqi wato *War Bonus Commissioner*, shi ya fara kai gaisuwar godiya ga Sarkin Zazzau Aliyu Xansidi a watan Nuwambar shekarar 1918.[1] Yaqin ya qare a ran 11 ga Nuwamban shekarar 1918. Ya zo ya yi godiya da tallafin da lardin Zazzau da Arewa suka baiwa Ingila a lokacin yaqi. Ko shakka babu 'yan Arewa sun baiwa Ingila taimakon kuxi da mutane a lokacin yaqi. Ko shakka babu 'yan Arewa sun nuna bajinta ta inna-naha a lokacin wannan yaqi. *Sir C. R. Niven* wani masanin tarihin Nijeriya ya ba da shaidar qwazo da suka nuna, ya ce sun sha wahala, sun kuma yi hasarar mutanensu da yawa. Amma sun nuna gayar jaruntaka.[2] Domin haka ne *Sir Renton* da Janar *Cunliffe* suka taso takanas daga Ingila don su zo su yi godiya ta musamman, ga Sarakunan Arewa da jama'arsu.

Waxannan manyan sojoji sun zo ne domin tabbatar da godiyar Ingila bisa yadda shugabannin Arewa da jama'arsu suka mara mata baya, a lokacin yaqin duniya na farko. Saboda haka ne sai shugaban rundunar sojojin ya kawo masu ziyarar ban girma.

A watan Maris na shekarar 1919, Janar Cunliffe da jama'arsa sun kai wa Sarkin Zazzau Aliyu Xan Sidi ziyarar ban girma. Janar xin ya nuna godiyarsu bisa yadda aka taimakesu da kuxi da kayayyakin yaqi da dakarun yaqi. Wannan ziyara ta faranta wa Sarkin da jama'arsa rai ta kuma qara danqon zumunci tsakaninsu.[3]

Ko da yake Turawan Ingila suna Mulkin Mallaka a wannan lokaci, amma saboda muhimmancin abubuwan da 'yan Arewa suka yi masu game da isasshen goyon baya da suka nuna sun qara masu kwarjini da daraja a idanun Turawan Ingilishi. Abin da Nijeriya ko kuma Arewa ta yi wa Ingila, tarihi ba zai manta da shi ba. Kamar yadda muka yi bayani idan batun aikin soja ne, Turawa 'yan Arewa suka sani suke kuma qauna, ba domin komai ba sai don qwarewarsu da haziqancinsu tare da rashin tsoron su in dai batu na yaqi ne.

Ya kamata aji yadda sojojinmu suka gwabza wancan yaqi na Is'Afrika da irin bajintar da suka nuna wajen wannan mummunan yaki. Farabiti Abdu Kano mijin Shattu yana xaya daga cikin sojojin da suka yi yaqin duniya na Xaya da na Biyu.

---

1 *Provincial Gazetter*, shafi na 36.

2 C. R. Niven, *Labaran Nijeriya*, Norla Zaria, 1955, shafi na 101

3 *Zaria Provincial Gazetteer*, shafi na 38

Ya ga irin hatsarorin da sojammu suka shiga da kuma irin bajintar da suka nuna. Wannan jarumi ya bada labarin wancan tsohon yaqi na 1914 – 1918, da irin hatsarorin da shi kansa ya shiga. Haka kuma da shi aka yi yaqin 1939 - 1945. Ga labarin:

"Yaqin da ai ko kusa ba a gwada shi da yaqin yanzu. Duk yaqin da muka yi a Is'Afirka a qasa muka yi shi, soja a qasa, Turawa a qasa, lebura a qasa. Kowa kuwa yana xauke da ful-macin-oda. A gama da yanzu da ya ke komai za a yi sai cikin mota? Dubi mu ma yanzu daga bariki zuwa nan sai aka kawo mu cikin mota. Haka muka yi wannan yaqi dai da Italiyawa. In an ji abokan gaba, sai a bi da mota, sai an kusa da su a sauka, a fara yaqi. Da kuwa sai a bi da gudu. Kuma wajen abinci yanzu ai daxi a ke sha. Da mun tava yin kwana huxu ba abinci, sai ganye mu ke ci. Kuma kowane irin ganye aka xiba, ba tara, sai kawai a dafa a sa gishiri. In ka sami ganyen turgunnuwa, ko naman gwari, ai wannan ya fi qarfin farabiti, sai a kai wa keftin.

"Maganar fa wancan tsohon yaqi na Is'Afirka na ke yi maka, ba ta wannan yaqin ba. A wancan yaqi dai, da muka tashi daga Mombasa, za mu Tanganyika, sai muka zo wani fili a gindin kuka. A nan muka yi kwana 14 muna yaqi ba dare ba rana. A nan aka harbi Samanja Bukar Mandara, yana nan Kaduna yanzu.

"Ana nan ana yaqi ashe Jamus harsashi ya qare. Ran nan da asuba sai muka hau musu da ihu da banati. Sai kwamandansu ya fito, ya xaga farar tuta. Abin da muka kama ran nan wajensu jan Bature 750, bindiga 350, mairuwa tamanin, bom xari, duk a rami muka tarad da su. Kwamandansu ya ciji baki ya ce, "Allah ya ba ku soja, mutanen Nijeriya!" A wannan yaqi Jamus ba abin da su ke tsoro sai sojan baqin mutum.

"Mazaje sun wuce! Samanja Mani Zazzau shi ke zama guguwa, sai ya tashi, ya bi inda Jamus su ke, ya gano, ya zo ya ba da labari. Da muka wuce gindin kukan nan da mil 12, sai aka harbi Dogon Yaro. Ga shi ya mutu, amma ya tsaya cif, bai faxi ba, saboda tambaya. Sai da Turawammu suka zo, suka kwantad da shi. Shi kuwa Bazabarme ne. Sabo da wannan jaruntaka tasa yanzu sunansa ba inda bai kai ba. Ga hotonsa nan a filin Dogon Yaro na Zariya. Har Ikko akwai hotonsa. Har Nairobi akwai.

"In an gamu an rikice, sai a yi ta harbi kawai, ba a san inda harsashi ke nufa ba. Kuna tare da abokinka, ka ga an kashe shi. Sai kawai ka ture shi ka ci gaba da harbi. Wani a harbe masa qafa, wani a harbe masa hannu, wani a huda cikinsa.

"Ran da muka tashi da Turawammu kuma za mu Darassule (*Dar es Salam*), sai Jamus suka tsinke wayarmu ba a sani ba, suka qulla da tasu. Sai suka buga waya wajen manyan Turawammu, suka ce a kawo musu gudummawa, wai ga Jamus za su halaka su. Shi ke nan, manyan Turawammu na hedkwata suna

tsammani mu ke neman taimako, sai suka suka turo mutane, ba a san Jamus ne ke magana ba. Ran nan a cikin bataliya guda tamu mutum talatin kawai suka tsira. Saura duk Jamus sun kashe su. Kai, yaqi xan wayo ne, ba na qarfi ba ne!

"Daga Darassule kuma da muka nufi Lindin a wannan tsakani aka harbi Samanja Hazo a diddige. Samanja Mamman Jima Mai-kan-kura, shi kuma da ya ga wuta ta yi yawa, sai ya yi laya ya har mutanensa. Saboda da haka har ana yi masa zambo.

"Da za mu fita, Auta Kwana guga abokina ya ce, mini, "Yau zam mutu!" Haka kuwa aka yi. Ana zuwa, harbin fari aka kushe shi.

"A hanyar Darassule nan ma an sha yunwa. Sai ka ga mutum na kira abinci abinci, har ya mutu. Ga ruwa kana xauke ba ka da ikon sha sai am ba da oda. Nama da biskiti ga su kana xauke, ba ka da ikon ci, sai am ba da oda. Daga Darassule aka ce mu bi Jamus Ijif (Masar). Amma baturen da mu ke kira Mai Baqar Xamara ya ce mu komo gida hakanan, abin da muka yi ya isa. Ka ji dawowarmu gida. Ka ji labarin tsohon yaqi na Is'Afirka"[1]

Ya kamata a ji yadda sojojinmu suka gwabza wancan yaqi na Is'afirka da irin bajintar da suka nuna wajen wannan mummunan yaqi. Farabiti Abdu Kano mijin Shattu yana xaya daga cikin sojojin da suka yi yaqin duniya na Xaya da na Biyu. Kuma kusan duk jaruman da ya bada labarinsu an san su a garin Kaduna kamar Samanja Bukar Mandara. Shi ko Samanja Mani Zariya, Mai Uwar Dawa da muqamin Keftin ya zo Kaduna ne a qarshen yaqi. duniya ta ga irin hatsarin da sojojinmu suka shiga da kuma irin bajintar da suka nuna. Wannan jarumi ya bada labarin wancan tsohon yaqin na 1914-1918, da irin haxurran da shi kansa ya shiga. Haka kuma da shi aka yi yaqin 1939-1945.

Jarumawan Yaqi

Tun a Yaqin Duniya na Xaya ne aka tsinke da 'yan Arewa wajen nuna bajinta da jaruntaka a wajen yaqi. Akwai sojoji da yawa waxanda suka nuna wa duniya jaruntaka, waxanda suka fito daga sassan Arewacin wannan qasa. Bayan yaqin duniya na Xaya ne garin Kaduna ya bunqasa da tsofaffin sojoji. Alamisali, akwai Nakauru da Manu Zariya waxanda har muqamin Keftin suka samo a wannan yaqi.

Shi Keftin Na Kauru mutumin Birnin Kano ne, yana xaya daga cikin mutanen farko da suka shiga aikin soja a Arewacin Nijeriya. Ya kuma nuna bajinta qwarai, yana xaya daga cikin Baqar Fatar farko da suka xaura muqamin Keftin.

Wannan gwarzo bai san wargi ba. Wajen Na Kauru babu ruwan hukunci da launin fata, don haka ya ladabtar da Turawa da yawa. Saboda ya kan sa a yi wa

[1] GTK Ta 88, Mayu 1943, shafi na 3-4

Turawa bulala idan sun yi laifi ba abin ku zo ku gani bane a wajen, Xa Ba Bara Ba.'

Keftin Manu Zariya mutumin Zariya ne. Shi ma bajintar da ya nuna ta ba shi muqamin Keftin a yaqin duniya na Farko. Labarin wannan dakare akwai shi da ban mamaki, domin an cewai shi mutumi ne wanda baya jin harbi a fagen fama. Saboda haka duk inda ya ratsa, sai ya bar gawarwakin Jamusawa ruxuxu a kwance sun sha dalma. A wani lokaci kuma an ce sai ya bari sai jama'ar 'Hitler' sun gama harbe-harben da aka hore su da yi, kafin ya nuna masu idan wajen kashewa ne, to, ai ya yi masu nisa. Farabiti Abdu Mijin Shattu ne ya bada labarin ya kan zama guguwa ya gano inda Sojan Jamus suke ya bada labari. An ce Xamarun da wannan Xantaliki ya yi amfani da su a lokacin yaqi suna nan a Gidan Ajiye Kayan Tarihi na sojoji na Kaduna.

Saboda irin wannan halayyar tasa da kuma yawan Jamusawan da Keftin Manu Zariya ya kashe, sai Turawan Ingilishi na shakkarsa suna yi masa kirari da laqabi da *King George* wato Sarkin Ingila. Jamusawa ba su da katavus inda na Manu yake. Halayyar irin yaqinsa daban take da ta sauran sojoji da kuma irin abin al'ajabin da wannan xan tahaliki ke nunawa, sai ana yi masa raxe-raxin cewa wai aljana yake da ita, don haka ne ba ya jin harbi. Wannan ya sa har kirari ake yi masa da "Na Manu Mai Uwaddawa. " Saboda yawan jinin da ya zubar shi kansa sai da ya xan tavu, da ya komo Kaduna ya zauna da Mai Damusa har qarshen rasuwarsa. Shi Mai Damusa jarumi ne mutumin qasar Chadi, kuma qwararren sojan Igwa a wannan zamani, shi ma ya yi bajinta qwarai da gaske.

Garin Kaduna ga qara bunqasa da sojoji bayan qarshen wannan yaqi. duniya ta sami zaman lafiyana shekara ashirin sai yaqin duniya na biyu ya varke. A wannan yaqi kuma sai aka ce 'yan Arewa ga ranarku!

Yaqin Duniya na Biyu

Ran uku ga Satumban shekarar 1939 aka fara yaqi tsakanin Ingila da Jamus, wannan shi ne varkewar yaqin duniya na Biyu wato yaqin Hitler. A wajen yaqi Jamusawa na son su ci duniya da qarfi da yaji, saboda haka ya zama tilas a hana su cimma muraxin su da tsinin mashi. Don kada su mallaki duniya su bautar da 'yan-Adam. Wannan shi ne maqasudin yaqin duniya na Biyu. Ko kaxan Jamus ba kanwar lasa ba ce, tana da qarfin soja sosai, sai an dage za a karya ta. Wannan ya sa tilas a yi mata taron dangi. A nuna mata Sarkin yawa ya fi Sarkin qarfi.

Saboda haka sai qasar Ingila da qasashen mulkin ta, da abokanta kamar Amurka, da Rasha, da Sin suka taru suka murqushe ta a shekarar 1945. Wannan yaqi ya watsu a duniya, inda yaqin bai shafa ba sai Amurka ta Arewa da ta Kudu. Wannan yaqi ya janyo hasarar rayukan miliyoyin jama'a, an naqasa mutane miliyan da dama, an kuma varnata dukiyoyyi masu yawan gaske. A wannan yaqi 'yan Arewa sun nuna bajinta da jarumtaka sun kuma samu yabo.

Rex Niven ya ce a wannan yaqi Nijeriya ta ba da taimako iri uku:

> *Ta ba da kayan yaqi, kamar su manja, da qwara, da gyaxa, da kuza, da auduga, da kwal, da katako, da kayan gini, da igiya da abubuwa masu yawa da aka yi a qauyuka don sojoji su yi amfani da su.*
>
> *Nijeriya ta yi taimako da mutane da yawa don yaqi. Dubbai sun shiga soja, wasu sun shiga sojan sama, wasu na ruwa. Dubbai sun yi aikin gyaran filayen jiragen sama da hanyoyin mota da aikin kuza. Soja sun yi yaqi a East Africa, da suka kori Italiyawa a qasar Habasha. Sun yi yaqi a Runduna ta 81 da 82 a Burma, da suka kori Japan daga Burma. Da yawa an xauke su a jiragen sama aka sake su a bayan layin sojan Japan suka karkashe su suka yi musu varna. Irin waxannan su ake kira "Chindits. " Sun kuma yi yaqi a Masar da Afirka ta Arewa da qasar Italiya.*
>
> *Na uku, Nijeriya ta zama ita ce babban gwadaben sama na xaukar soja da kayan yaqi zuwa Masar, Rasha, Indiya da Sin. An daxe Ingila ba ta sami bi da jiragen ruwanta ta Bahar –Rum ba, tilas sai an zagaya Afirka ta Cape of Good Hope. Wannan doguwar hanya ce, saboda haka ya fi sauqi a sauke soja da kayan yaqi a GolKwas da Nijeriya, daga nan a tafi da su zuwa Masar ta jiragen sama. Ta wannan hanya ne ake kaiwa sojan Ingila da ke Afirka ta Arewa kayan yaqi, da kuma gavar Masar. Filayen jirgin sama na Nijeriya sun taimaka wajen cin yaqi.* [1]

A tsakanin shekarar 1942 zuwa shekarar 1944, fiye da mutane dubu xari da goma (110,000) aka tura aikin kuza daga lardunan Arewa don su taimakawa Ingila a lokacin Yaqin Duniya wajen samar da kuza. Ta nan ma Nijeriya ta taimaka da kuza wadda ake amfanin da ita wajen qera kayayyakin yaqi iri-iri.

A lokacin Ingila ta rasa Qasar Malaya wadda Japanawa suka qwace. Saboda haka aka tashi haiqan wajen neman kuza don a agazawa Ingila a lokacin yaqi. Kusan mutane dubu goma sha-xaya (11,000) masu haqar kuza, suka halaka saboda matsanancin yanayin wajen wannan aiki. Mutane da yawa suka rasa rayukansu saboda wata tsutsa wato 'jigger' wadda ke cin sawun qafafu, a dalilin haka mutane da yawa sun hallaka. [2]

A nan ma Arewa ta taimaka wa qasar Ingila da isasshiyar kuza, wanda hakan ya taimaka wajen cin nasarar yaqi da Hitler. A wannan lokaci ne qaimin mawaqa ya tashi, inda suka riqa waqe kuza, don 'yan Arewa su himmatu wajen samar da

---

1 C. R. Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi na . 110-111

2 Daily Trust, Thursday July 3, 2008, shafi na 56

kuza, duk kuwa da irin wahalhalun da ke tattare da wannan aiki. Ga xaya daga cikin waxannan waqoqi:

Waqar Kuza

To, bismillahi zam fara waqa,
Ina fara waqa ta aikin kuza

Ina duk mutane marasa sana'a
Ku zo, ga sana'a ta aikin kuza!

Ina masu yawo na banza a titi?
Rabo na kiranku wurin yin kuza!

Bargo biyu ne ga kowane qato,
Abinci da iccen wuta don kuza.

Akan ba su satinsu duk Asabar,
Su kan dinga murnarsu, 'ya'yan kuza

Xalibansu wasa dare da rana,
Dare ne na hutun mutanen kuza.

Ina wani lebura ya sami ciwo
Akwai likitoci na aikin kuza.
Babban taimako ne bias wanga yaqi,
Mu kore masiba da aikin kuza!

Ina bindigoginku, ku lebura?
Ku ce mini, "Digarmu ta yaqin Kuza!"

Mu sanya asara wuyan Hitler,
Mu zam bige Berlin da qarfen kuza.
Mu zam cire tuta ta azzalumai,

Mu zam kafa tamu dalilin kuza.
A ran nan da murna wurin Mista Churchill,
Wazirinmu, shi ne ya gano kuza!

Jiragen ruwa hard a mota ta yaqi,
Jiragen sama duk da qarfen kuza

Ku ce bindigogi da harsashi duk,
Ku san magani c eta tsatsa, kuza!

Alhamdu Lillahi na cika waqa,
Da na cika waqar jawabin kuza.

Muhammadu 'Yola, Kano, 1944.

Arewa Nagge daxi goma. A daidai lokacin da Arewa ke bai wa qasar Ingila kuza, sai Sarkin Ingila ya aiko wa Sarakunan Arewa da saqo cewa su noma gyaxa, in kuwa ba haka ba cin nasarar wannan yaqi da Hitler zai faskara.

Gyaxa Ta Fi Harsashi

A wani rikirkitaccen lamari da ya afkowa wa qasar Ingila da abokanta shi ne fahimtar cewa ba za'a akai ga nasara a yaqin Hitler ba, sai an sami mai, wanda a wancan babu inda za'a same shi a duk duniya sai Arewa. Saboda ganin haka ne Sarkin Ingila ya aiko da saqo na musamman ga Sarakunan Arewa da yana buqatar Arewa ta xuqufa ta noma gyaxa domin a samu isasshen mai wanda zai taimaka wajen cin nasarar wannan yaqin duniya.

An kuma nuna wa jama'ar Arewa muhimmancin wannan buqata ta mai da ke fuskantar Ingila. Domin kuwa mai babban abu ne ga xan Adam. Akwai abinci da yawa waxanda ba su yiwu wa sai da mai. To, duk hanyoyin da ke kawo wa mutanen Ingila mai a da, sai suka yi matuqar wuya a lokacin wannan yaqi. Babbar hanya guda ce ta rage wadda itace samarda mai daga Nijeriya ta Arewa.[1] Saboda haka ne sai aka buqaci 'yan Arewa da su naxa gammo su xauki Ingila dukanta su ba ta mai har ta ce taqoshi. Ta haka kowa zai san Nijeriya bata haifi ragaye ba.[2] Saboda ko neman askarawan yaqi bai tayarwa Ingila rai ba kamar neman man gyaxa.

---

[1] GTK Ta 82, 31 ga Maris 1943

[2] GTK Ta 82, 31 ga Maris 1943

Haqiqa ana buqatar gyaxa qwarai daga Arewa. Domin abin ya yi tsanani sosai domin har ya kai ga Gwamna ya xauki Razdan guda musamman, Commander Carrow, wanda ya yi joji a Kano, an kuma san shi da Karo, shi aka naxa Sarkin Noman Gyaxa, harda waxansu Turawa ma waxanda ke aikin soja, am maida su wajen wannan babbar daga ta neman gyaxa. Har ila yau Wakilin gwamnan makaranta kuma ya umurci Turawan makaranta duk su taimaka wajen bayyanawa jama'a abin da ake ciki.[1] Saboda haka duk inda mutum ya ajiye wannan al'amari sai ya ga ya wuce nan. Matsayin gyaxa da amfaninta ya wuce abubuwan da aka faxi wajen nemanta ido rufe!

Gwamna kuma sai 'ya yi doka, ya ce ba a yarda kowa ya fidda gyaxa daga qasashen Nijeriya ta Arewa ba, ko ya xauki gyaxa daga qasar wannan Razdan ya kai ta wancan ba, sai in zai kai wurin aikawa Ingila ne. Ba a ma yarda mutum ya sa gyaxa a jirgin qasa, ba sai fa in za a aika da ita tashar jirgi zuwa Ingila,[2] Saboda haka matsayin gyaxa a wannan lokaci ya wuce duk yadda aka zata, ta fi komai daraja. Kai har ma ta fi harsashi a fagen yaqi saboda Sojoji da bindigogi da sauran makamansu duk suna buqatar man gyaxa. Ba za su iya yin komai ba in babu gyaxa. Domin haka ne ake cewa da manoman gyaxa da masu qera makamai duk darajarsu xaya ne.

Sarakuna sun yi qoqari tare da jama'arsu wajen samar wa Qasar Ingila isasshen kuza wanda ya taimaka mata wajen cin nasarar wannan yaqi. A wannan yaqi ma duniya ta sake tsinkewa da bajinta da jaruntakar 'yan Arewa a fagen yaqi. Saboda haka ya kamata mu tuna da waxannan sojoji. A wannan yaki ne, sai gyaxa ta zama 'harsashin' harbin Hitler!

Mu Noma Gyaxa, mu ka da Hitler

Ina Manoma da Masaqa? Ina Maxunka da Marina? Ina 'yan Kasuwa da Mahauta? Ina Sarakai da Fadawa? Ina Malaman makaranta da 'yam Makaranta? Ina Malaman Ofis da yaran Turawa? Ina 'yan Hayan basukur da na mota? Ina Maroqa da 'yan Raraka? Dukanku gwamnan Nijeriya ya ce ya gaishe ku. Bayan gaisuwa, ya ce a gaya maku bai xauke wa kowa ba, babba da yaro, a yiwa Ingilishi gudummawa da gyaxa! Sana'ar duk da mutum ke yi a Nijeriya, Gwamna ya ce yana so ya gama da noman gyaxa. Ingila naba soja makamai, su Amirka naba soja makamai, to, mu kuwa bana an ce ludayi ya juya gare mu, mu aika wa Ingilishi da gyaxa! Jama'a kun sani fa, sai an sha qari ake iske zuma. To, mu miqe, mu xauki hauya, mu tono nasara![3]

---

1 *Ibid.*

2 *Ibid,*

3 GTK ta 82, 31 ga Maris 1943

Haka kuwa aka yi, 'yan Arewa sun amsa kira gaba xaya, Arewa ta xau hauya ta tono wa Ingila nasarar yaqi da Hitler. A tarihin Nijeriya babu kayan gona kona ma'adinai da ya kai darajar gyaxa a lokacin yaqin duniya na Biyu. Ko auduga wadda aka shimfixa hanyar jirgin Baro zuwa Kano ba tayi tashen gyaxa ba. Sarakuna da Turawan Mulki sun tashi tsaye domin ganin kowa da kowa a Arewa ya duqufa ainun wajen noman wannan aba mai darajar gaske. A dalilin haka ne Sarakuna bakwai suka yi taro na musamman a birnin Kano tare da Lord Swinton, Wazirin Ingila a Afirka ta Yamma.[1]

Ran 4 ga Afrilu 1943 Lord Swington, Wazirin Sarkin Ingila mai kula da qasashen Afirka ta Yamma ya sauka Kano daga Maiduguri. Ya iske Sarakuna bakwai sun taru suna jiran zuwansa. A wannan taro ga Sarkin Musulmi Alhaji Abubakar da Wazirinsa Abbas, da Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayaro, da Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo, da Sarkin Daura Alhaji Abdurrahaman, da Sarkin Haxeja da Kazaure da Gumel. Kowanensu yana tare da 'yan Majalisarsa. Manyan Turawa sun hallara harda Sabon gwamnan Kaduna Mr. Patterson da Razdan na Kano Commander Carrow, kuma Sarkin Noman Gyaxa.

A washegari ran 5 ga Afril suka taru a layin Alqalin Alqalai, bayan an natsa sai lord Swinton ya shiga bayani akan abubuwa da dama game da yaqin Hitler. A cikin bayaninsa ne ya bayyana irin mugun tanadin da Hitler ya yiwa duniya, idan ya sami nasarar wannan yaqi. Wanda shi ne ya bautad da kowa duk jama'a su bauta masa, ya zama babu mai wani tasiri sai shi, sai kuma abin da ya ce.

Bayan wannan, Lord Swinton ya sanarda taron nan cewa lalle bana ana buqatar gyaxa qwarai gaba da kima. Za a kuwa sayeta da daraja matuqa. Ya bayyana cewa sha'anin gyaxa muhimmin a bu ne qwarai domin ana yin abubuwa da yawa da ita waxanda suke suna daga cikin babban taimako na samun nasarar wannan yaqi. Idan kuwa mun lura, wannan sassauqan abu ne a qasar nan tamu, domin ko da ma can gyaxa tana daga cikin abubuwan da ake samu a Nijeriya har ma waxansu mutane da yawa da ita suke biyan haraji. Saboda haka aka umurce mu da qara yawanta, yadda za ta wadata, mu kammu mu yi amfani qwarai wajen samun kuxi sa'an nan kuma ga shi mun taimaki yaqi. Har a cikin maganarsa ya ce, "wanda ya noma gyaxa, da soja wanda ya ke fagen fama xaya suke wajen taimakon neman nasarar wannan yaqi".[2] Wannan ba qaramar Magana ba ce.

Shi aiki baya yiwu wa sai da himma. Saboda haka Lord Swinton ya ce ya umurci Sarakuna da su zaga gonakin talakawa domin wannan zai qara musu himma wajen noma gyaxa har ta isa kamar yadda Sarkin Ingila ya umurce mu.

---

1 *Ibid.*

2 *Ibid.*

Sa'ad da ya Lord Swinton ya gama bayaninsa sai Sarkin Musulmi ya tashi ya ce, "Mun ji, mun karvi umurnin Sarkin Ingila. Za mu ci gaba da qoqari matuqa. Ba za mu zauna ba har gyaxa da abinci su wadace mu, mu da soja duka, in Allah ya so, kamar yadda ake buqata".[1] Daga nan sai Turawa suka fita, suka bar Sarakuna suka ci gaba da shawara a tsakaninsu yadda za a shirya al'amarin sosai har a cimma buqata.

A wannan taro Lord Swinton ya bayyana dalilin wannan yaqi da Hitler da kuma wajibcin ganin an yi nasara akansa da abokansa. Amma koda yake bai fayyace dalilan da suka sanya qasar Ingila buqatar samun isasshiyar gyaxa wurjajan, ba amma ya nuna mahimmancin wannan aba da cewa da soja da yake yaqi a fagen fama, da manomin gyaxa duk matsayinsu guda ne. Watau dai in ba gyaxa, Ingila da abokanta ba za su ci nasarar yaqi da Hitler ba. Saboda haka za a fahimci cewar akwai abubuwa muhimmai da qasar Ingila ke yi da gyaxa a wancan zamani wanda ba a fito fili an bayyana ba.

Saboda mahimmancin gyaxa a wannan lokaci kowa da kowa sai ya duqufa wajen nomanta har Turawa ma ba'a barsu a baya ba. Maganar gyaxa babban al'amari, 'yan Kwaleji ma ba a qyale su ba. Shugaban Kwalejin Kaduna Mr. Mort ya faxawa 'yan Kwalejinsa akwai amfani guda biyu ga noman gyaxa. Na farko shi ne taimakon yaqi. Na biyu kuma ga kuxin da za'a samu wajen sayadda ita. Saboda haka ya sayawa 'yan Makaranta faretani guda xari da garma ishirin don wannan aiki. Ya ce da su su tafi noman gyaxa maimakon filin wasa. A dalilin haka ne noman gyaxa a Kwalejin Kaduna ya tashi haiqan. Kowa a Arewa sai ya duqufa wajen noman gyaxa 'yar Churchill. Saboda haka ba wanda ya yi mamaki da buhunta ya kai sule ashirin sai kuma hauhawa ya ke yi. Gyaxa kibiyar harbin Hitler.[2]

Qasar Ingila ta aiko da neman taimako cikin gaggawa ga Jihar Arewa. A lokacin da Yaqin Duniya ya turnuqe, sai aka lura sojojin Ingila da qawayenta na buqatar gyaxa idan ana so a sami galabar wannan yaqi. Ana amfani da gyaxa, ana kuma sarrafa ta wajen yin abubuwa masu yawa da ke da amfani ga sojoji da kayayyakin yaqi iri-iri. Saboda haka ne sai Jihar Arewa ta tashi tsaye wajen bayar da isasshen taimako da gyaxa. Ingila ta nemi taimako ta kuma samu da gaggawa.

Sarakuna sun yi amfani da kafafen yaxa labarai, musamman ta jaridar ta wajen yin kira ga jama'ar Arewa da su duqufa wajen shuka da noman gyaxa a duk faxin Arewa, kuma a wannan kira ne, Editan Jaridar Gaskya Ta Fi Kwabo ya rubuta sharhinsa akan muhimmancin noman gyaxa inda ya ce:

---

1 GTK ta 88, Mayu 1943

2 *Ibid.*

"Subhanallahi! Malam, yaya aka fara ne har yanzu gyaxarka ba ta isa fagen yaqi ba? Kada mu yi azumi kuma mu kurkure baki da ruwan toka! Mun share gonaki, mun haqe, mun shuka gyaxa, mun tone, don mu taimaki Ingilishi, to, yaya kuma za mu ji kyuyar kai ta fuloti?

"Jama'a, ku lura, wannan al'amari na gyaxa ba domin kuxi kaxai a ke yinsa ba. Abin da za mu sa a rai shi ne taimako. Mu yi taimako da gyaxa, maza-maza a ka da Hitler. Mu bar neman wuri ya ja wuri, nasara ita ce babbar riba. Mu mutanen Nijeriya muna iya hayewa, ko babu gyaxa. Amma a wannan kokawa, in Ingila ita ta rasa gyaxa, abu ya vaci. Saboda haka ya kamata mu yunqura yanzu-yanzu mu kai gyaxarmu fuloti, mu taimaki 'yanuwa na bakin daga, kada mu yi kuwa bayan hari.

"Mu kai gyaxa bakin daga, fuloti, mu nuna godiyarmu ga Maxaukakin Sarki Allah Wanda Ya yi mana wanna zavi. Ka ga zavin da Allah Ya yi mana, maimakon mu tashi da kanmu, mu je fage, mu sai da rai mu nemo 'yanci, sai ga shi Allah Ya nufa mu sai da gyaxa shi ne fansar rayukammu.

"Turawa tun daga nan har Ingila sai godiya su ke yi, suna cewa Afirka ta Yamma, tun ba Nijeriya ta Arewa ba, tsaye take da himma a kan taimako. Qasashe da yawa kullum sai kuxi su ke tarawa, suna bayarwa gudunmawar yaqi. Waxansu na cewa a sayi jirajen sama da kuxinsu don su ji daxi, su ga su ma sun ba da sandan dukkan Hitler. To, yaya manoma, waxanda suka yi xamara da damina don su ba da gyaxar dukkan Hitler, za su kuma kai ta rumbuna?

"To, manoma, in ana ta kai fa ba a ta kaya. Mutum ya kan shuka alheri don ya girba ne, daga shi har 'ya'yansa. Ku tashi, mu aika da gyaxa fuloti! Wannan alheri muna shuka shi ba domin sulallan da za mu samu ba, sai dai domin kammu, domin bayan yaqi mu ci 'ya'yan wannan alheri da muka shuka. Alheri da taimako kamar dawa ne, sai wanda ya shuka shi zai girba.

"Da manoman gyaxa, da maqerin makamai a Ingila, duk darajar aikinsu xaya take ga wannan yaqi. To, in haka ne, da wane suna za ka kira maqerin makamai, wanda ya qera makami tuli sa'an nan ya kwasa ya kai gidansa ya voye a rumbu, ya qi ba mayaqa a fagen fama? Irin sunan da za ka kira wannan mutum, da irinsa kuma za ka kira wanda ya noma gyaxa ya kai ta rumbunsa ya voye.

"Haqiqa wannan abin farin ciki ne a gare mu, tun da Turawa da bakinsu su ke yaba amincimmu a yanzu sa'ad da duniya ke cikin wuta, lallai ne nan gaba in an ka da Hitler mu ne gaba-gaba wajen shan zuman nasara.

"Ya kamata mu qara maimaita muku, akwai fa zuma bayan nasara, amma fa kafin a kai gare ta har a sha, kowa sai ya xanxana harbi. Abin da mu ke so, ko bayan yaqi. Turawa da kansu su ce, "kai, mutanen Nijeriya kowa ya yi abuta da su ya huta. " Mu kuma sa'an nan ne za mu ji daxin zura ido su nuna mana halin girma. Ka san wanda ya taimake ka xibar zuma shi ne masoyinka, ba wanda ya taimake ka sha ba.

"To, ina Hakimai da Sarakunan kauye, ina malaman Dagatai da sauran ma'aikata? Kamu ya zo gare ku! Sai ku miqe sosai, ku shiga gaya wa jama'a gaskiya! Ku ji tausayin 'yan uwanmu, soJan Ragamar Nijeriya, suna jiran gyaxa don su qara makamai. Ku ji tausayin mutanen Ingila, waxanda ke tsaye ba dare ba rana don su farauto mana 'yanci. Ga su can sun buxe baki wajen Nijeriya suna jiran gyaxa. "To, jama'a don Allah a taimaki zumunci, kowa ya taimaki wani Allah Ya taimake shi. "[1]

duniya mai ya yi. Ana wata ga wata nan. A lokacin da yaqin Hitler ya yi qamari sai buqatar gyaxa ta taso haiqan saboda abubuwa da yawa da ake amfani da ita. A wannan lokaci na qaqa-ni-kayi da qasar Ingila ta shiga, babu inda yake da arziqin gyaxa a duniya kamar Nijeriya ta Arewa, qasa mai albarkar nagartattun jama'a da arziqin gona da ma'adinai. Saboda haka sai Qasar Ingila Arewa da ta taimaketa da gyadar harbin Hitler. Saboda a wannan lokaci da manomin gyaxa da maqerin makamai duk darajarsu xaya!

Jawabin da Lord Swinton ya yi a lokacin da ya yi taro da Sarakuna sai aka bugashi a qaramin littafi aka rabawa jama'a don kowa ya farga ya fahimci wannan sabon al'amari da ya zo. Tun kafin wannan, Wazirin Sarkin Ingila ya yi taro da Sarakunan Arewa bakwai akan batun gyaxa Turawan Mulki ba su voye maitarsu ba. Don kuwa a ranar da ya buxe Wayar Iska wato Wireless Radio a birnin Kano a ran 1 ga Afrilu 1944, Razdan na Kano Commander Carrow, Sarkin Noman Gyaxa a cikin jawabinsa a wannan rana ya ce:

"Ka da dai im vata muku lokaci, jama'a don na tabbata kuna alla-alla kuji jawabi daga Ingila cikin wayar Iskarku. Duk da haka, kafin dai in qara jawabina, ban cika aikina ba sai fa inna ambaci wata kalma wadda ta ke muhimmiya ga jama'ar Kano, ita ce GYAXA. Wazirin Ingila da ke zaune a Afirka ta Yamma, Lord Swinton, ya ziyarce mu a wannan maqo tare da gwamnan Kaduna, suka ce bana ma ana buqatar gyaxa mai tarin yawa, kuma lalle mu maida wannan qoqari na aikin gyaxa ya zama shi ne babban taimakommu na yaqi.

"Ni aka sake naxa wa Sarkin aikin gyaxa. Ina muku godiya, don cika umurni da taimakon da kuka yi na aikin gyaxa a wannan shekara da ta wuce. Na kuma tabbata a wannan shekara mai zuwa ma kowa zai yi taimako mai yawa, har ma ya fi na bara. Dukammu kowa ya kamata ya yi qoqari, kamar yadda sojammu na bakin daga su ke yi, idan muka yi haka, abin da mu ke fata zai samu, shi ne gyaxa mai yawa. Allah ya ba Sarkin Ingila nasara, amin".[2]

---

[1] GTK Ta 102, 5 ga Janairu, 1944, shafi na 5

[2] GTK Ta 102, 5 ga Janairu, 1944, shafi na 5

Saboda haka sai Sarkin Ingila bai yi qauron baki ba, sai ya aikowa Sarakunan Arewa da muhimmin saqo na shuka gyaxa don a samu isasshiyar da ake buqata don cimma galabar yaqi da ake gwabzawa da Hitler da abokansa. A wannan lokaci buqatar gyaxa kusan ta fi buqatar kuza wadda Arewa ke aikawa Ingila don kera makamai. A wannan lokaci har kwatanta gyaxa ake yi da albarushin bindiga da Iggwa.

A wannan lokaci mai haxarin gaske, sai Sarakunan Arewa suka amsa kiran Sarkin Ingila, suka kuma tsaya, tsayin daka don ganin an samu isasshiyar gyaxa da za ta taimaka ga cimma nasarar yaqi. A wannan lokaci ne ma Turawan mulki ke qarfafa noman gyaxa da cewa, manoman gyaxa a Arewa dai-dai suke da sojojin da ke fagen fama a wannan yaqin Hitler, wani mummunan yaqi da ake gwabzawa da Jamusawa da abokansu don a karyasu a tabbatar da adalci a duniya. Jama'ar Arewa tun fil azal, mutane ne masu biyayya ga Sarakunansu don haka suma suka duqufa wajen noma wannan aba mai daraja. Allah kuma ya taimaka Arewa ta fidda qasar Ingila a buqatar da take yi wajen neman dakaru, da kuza da gyaxa da sauran makamantansu.

Kiran Sarkin Kano:
Assalamu Alaikum
Jama'ar Kano!
Ya jama'ar Kano, Sarkin Ingila ya sake tambayarmu gyaxa bana, fiye da ta bara. Na gode wa manoma duka, waxanda suka yi gyaxa bara. Kuma ina buqata su qara qoqari bana, fiye da na bara, don taimakon yaqi. Allah Ya ba mu damina mai kyau, amin. Allah Ya ba Sarkin Ingila nasara, amin[1]

Sarkin Kano Abdullahi
12.4.44

Gargaxin
Sakkwatawa, lokaci ya yi!
Godiya ga Allah Ubangiji, Wanda Ya nufe mu da sake kawowa ga bana war haka, cikin aminci da zaman lafiya. Bara war haka ne Sarkin Ingila ya bixe mu mu noma gujjiya saboda sojojinmu, Allah kuma ya kyautata ya ba mu damina mai albarka, kunka noma ta mai yawa. An gode. To, bana kuma ya sake tambayarmu ita, sojojinmu har wa yau suna buqatar mai yawa, fiye da bara. Don haka na san asshe ku wagga buqata, gama mai shirin shiga ruwa tun daga tudu yake tuvewa! Tattalin noman gujjiya tun ga yanzu ake fara shi. Don haka nake faxakasshe ku tun yanzu. Ku shiga tsimi ku shiga dabara, ku fara tattalin iri mai yawa, ku qara manoma, ku yi niyyar cika umurnimmu, kamar yadda munka horeku kunka xauka

[1] *Ibid*. Afrilu 1944, shafi na 6

bara, don a samu a ida biyan buqatar duniya, a ka da azzalumai maqiyan adalci da xiyauci, da babbaqun arnan da ba su buqatar addinin gaskiya![1]

Abubakar

Katsinawa da Daurawa

Ya ku mutanen Katsina da Daura! Mun gode muku saboda qoqarin da kuka yi na ba da gyaxa. Har yanzu baqin yaqin nan bai qare ba, don haka sai ku tashi tsaye, ku qara himma. Gyaxa! Gyaxa! Gyaxa! Ita Sarkin Ingila ke buqata gare mu, fiye da ta bara. Sai mu amsa kira. Allah Ya sa gyaxarmu da za mu bayar, ta ida magiza! Allah Ya ba mu damina mai albarka, amin.

Sarkin Katsina Usuman
Sarkin Daura
Abdurrahman.[2]

Umurnin Sarkin Kano

Hakimai, Ku Mai da Himma!

Sarkin Kano Abdullahi Bayaro, bayan ya aza harsashin ginin sabon masallaci. Ran 12.4.44 ya yiwa hakimansa umurni mai qarfi, ya ce, "Na umurce ku, kowa ya gargaxi mutanensa su ninka noman gyaxarsu, fiye da yadda suka noma a bara. Ko da yake mun gode wa duk wanda ya yi gyaxa bara, bana kuma za mu qara godiya, fiye da ta bara, idan Allah Ya nufe mu da yinta. Kowannenku ya gargaxi a Burma da gaisuwa. Wato, in sun yi jawabinsu, shi fafai, akai shi can Hindu.[3]

Mutanensa a sannu, ba tare da tashin hankali ba, kowa ya yi gyaxa ganduna masu girmafiye da bara. Allah Ya nufa wannan gyaxa tamu ta bana ta kasance ita ce hanyar xaxxako saiwar azzaluman duniya! "[4]

A shekarar 1944 farashin gyaxa ya haura na bara. A Kano da Ringim da sauran Kasuwanni da ke hanyar jirgi kuxin ton xaya £1 (buhu 20/-). A wuraren da ke nesa da hanyar jirgi za a xebi yan kuxin sufuri. Amma Sarkin Ingila ya ce duk ko'ina kada ton xaya ya kasa £9 (buhu 15/-). Shuka gyaxa, ka kwashi kuxi jingim! Yi shirin noma tun yanzu.[5]

Ku Saurara Mutanen Argungu

---

1 GTK 10 ga Mayu, 1944, shafi na 4

2 *Ibid.*

3 *Ibid*

4 *Ibid*

5 *Ibid*, shafi na 6

Ingila tana nemammu da taimakon ba da gyaxa bana fiye da bara. An yabi qoqarinmu na bara. Amma ana neman mu qara himmatuwa bana fiye da haka. Ina fata in ganku cikin aikin gyaxa bana, lokacin da nake zazzagawa wurin rangadi. Muna roqon Allah Ya bamu damina mai albarka, yadda zan ga kun amsa wannan kira. Kun riga kun sani mai noman gyaxa da wanda ke xauke da bindiga a fagen fama girman xaya.

Ku yi himma, nasara ta kusa zuwa, in Allah Ya so!

Sarkin Argungu Isma'ilu[1]

Ina Mutanen Gwandu?

Jama'ar qasar Gwandu, ina sanasshe ku, Sarkin Ingila ya sake tambayarmu gyaxa bana fiye da ta bara. Don haka in buqatar ku qara qoqari, fiye da na bara, don taimakon yaqi. Allah Ya taimake mu, ya ba mu damina mai kyau da lafiya, ya ba Sarkin Ingila nasara, amin.

Sarkin Gwandu Yahaya.[2]

Ina Mutanen Yawuri

Ya jama'ar qasar Yawuri, babba da yaro duk ina gaishe ku. Bayan gaisuwa, ina tashin ku ne daga barci! Ku sani bara ba mu cika alqawari wanda muka yi ba, domin rashin sabo, da yawan sanyin qasa. Wato abin da muka yi bara ya zama hanya, ta lura da duk abin da take so, da wanda ba ta so. Don haka bana an bixe ta fiye da bara. To, sai ku qara qoqari mai yawa fiye da ta bara, don mu fita kunyar Sarkin Ingila. Allah Ya ba mu ruwa isasshe, ya ba Sarkin Ingila nasara, amin.

Sarkin Yawuri Abdullahi.[3]

Waqoqin Gyaxa

Jama'ar Arewa, mutane ne masu ilmi da fasaha iri-iri. Akan farkar da talakawa bisa kan kowane al'amari ta waqoqi iri iri. Domin ta haka ne ake karantar da su cikin hanzari kuma a sauqaqe. Saboda mutane ne masu kishin addininsu, qasarsu da al'adunsu ake samun jawo ra'ayinsu ta waqoqi, ba kuxi ake rarraba masu ba kamar yadda suke yanzu. Faxakar da jama'a ta hanyar waqa ya samo asali ne tun daga zamanin Shehu Mujaddadi. A lokacin yaqin Hitler an yi waqoqin soja iri-iri, amma a wannan lokaci babu kamar waqar gyaxa wadda mutane suka wallafa don su farkar da jama'a wajen nomanta ba don kuxi kawai ba, a'a domin a kai ga nasarar yaqi.

---

1 GTK Mayu, 1944, shafi na 6

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*, ta 113, 7 ga Yuni, shafi na 2

Waqar Gyaxa

Ku shibka gyaxa ku sami kuxin vatarwa.

Batunga da anka yo kowa shi ji shi,
Mu yo aniya mu bar neman gazawa.

Ku shibka gyaxa da dama, ka manoma,
Batunga da anka yo ku fada ma kowa.

Ku daina zama, ku tashi ku mai da himma,
Ku nemi wuri ku sa gero da maiwa.
Ku shibka gyaxa, gauna kuxi ta ke yi,
Ga wannan shekara, bana ba sakewa.

Ku nemi wuri ku sa gujiya manoma,
Ku san fa kuxi akwai daxin vatarwa.

Ga wannan zamani kowa ka aiki,
Shina samun abin da shi ke ajewa.

Ga yau samu shina gun masu aiki,
Mu shibka gyaxa mu bar neman sakewa.

Zama yau zamani ne wanda ya'zam,
Manoma su ka cin girma ga kowa.

Ku nemi hatsi, ku bar son yin fatauci,
Ku shibka gyaxa ku sami kuxin vatarwa.

Ku shibka gyaxa da kaxa, ku manoma,
Fataucin yanzu ba shi da tabbacewa.

Ga dauri hatsi da kuxin sun wadata,
Ga yanzu hatsi yana gun masu noma.

Fa Turawan qasa bana sun tsaya duk,
Batun noman gyaxa suka so ga kowa.

A nan jojin Gusau ya ce a shibka,
Gyaxa ga qasar Gasau kuwa da kuwa.

A Sakkwato duk jama'a sun ji wannan,
Jawabi, sun riqa bisa gask ituwa.

Qasar Gwandu an shada ma kowa,
Da Yawuri, Kwantagora kuna jiyawa.

Kasar Mina, Dungurun, da qasar Kafancan,
Ilori da Bida an shaida ma kowa.

Qasar Muri duk da Binuwai an yi doka,
Batun shibkar gyaxa, ba zave kowa.

Qasar Zazzau, Kaduna, qasar Kazaure,
Batun gwamnan Kaduna ku bar sakewa.

Qasar Katsina, su Funtuwa duk kuna ji?
Ku shibka gyaxa da gaske ku bar sakewa.

Kano, a faxa ma duk jama'a su shibka,
Amirul Muminina ya zo ga kowa.

qasar Daura da Barno a shaida kowa,
Batunga, a ji shi har bisa Adamawa.
Haxeja da Bauci an shaida ma kowa,
Batun shibkar gyaxa, bana ba sakewa.

Abin nan taimako ne gun mayaqa,
Ana yin bom, ana yin shel da mayin qadirawa.
Mu yo roqon ruwa gun Mai Iyawa,

Bama Allabu shi ka isam ma kowa.

Malam Isa na Sardauna Gusau, 1944

Waqar Gyaxa

Mun sami albishiri ta hanyar taimako, Yaqi shi qara nan da nan. A yi sammako,
Kowa shi xan kwasa zuwa daji, shi ko Sare itace, sassabe hakanan, shi ko
Kone, shi shibka gyaxa cikin fili nasa.

Manyammu sun hore mu, mu ko mun kula, Mun ba da kuxi daga kwabo har mai dala
Wasu sun yi soja, Wajen tufa mun baddala. Mun jimre tsada, Hausa babu tsumulmu'a.
Noma daxai kowa shina qamna tasa.

Babbar sawaba ta gare mu a ce gyaxa, Kowa fa ya san Hausa ak kantin gyaxa,
Ga halimmu Hansawa idan an gidada, Kowa xiyanci na garai a ga yai gyaxa,
Don taimakon nasara a kau gode masa.

Labudda rana taku sai daxa mun gani, Kunya ta raggo ta haqiqan mun sani,
Bana wanda bai yi gyaxa ba shi ka gunaguni, A mu kwashe kuxi cus mu bar shi da gunguni,
A yi lafiya kowa shi hau kuxi nasa.

Allah shi ba mu ruwa shi kyauta gyaxa kawa. A mu gundure Turai su sami gyaxa kawa!
Allah sai inda nufi, shi ba mu gudummawa, Da ruwa da ni'ima mai awa hakanan kawa,
Nasara ta gagganto shi sa sauqi nasa!

M. Alhaji Dogondaji Sakkwato, 1944

Waqar Gyaxa

Mutane gare ku na ke gargaxi! Ku farka ga barci, ku bar gyangyaxi
Ga qauli sahilu da babu daxi, Gama na gani za ku kwashi kuxi,
Idan kun yi humma ta noman gyaxa.

Riba guda biyu ce ba guda ba, Da noman gyaxa kun ga za ku ci riba,
Da noman gyaxa za a kore masiba Ta wannan kare wanda ke man fuba,
Ta qarya, idan kun yi noman gyaxa

Ga taimako wanda ankai man, Bature guda anka turo mana,
Ya zo don ya qarfafa zancen nana, Gama ya yi yawo, idan kun tuna,
Yana gargaxi don a noma gyaxa.

Wanda ya noma kadada xaya, Zai samu kuxi ya sau godiya,
Ta wanda ya noma ton sha xaya, Kamar ya yi bom a garin maqiya
Mutane ku qarfafa noman gyaxa!

Ayyururui! Bana za ai biki! Am buxe hanya ta yin arziki,
Ta noman gyaxa a cikin gonaki, Maqera, manoma, ku motsa ku ji,
Ku ne ussai na noman gyaxa.
Ka tambayi dagacinka, im ba ka gona, Ya ma qoqari tun kuna shaida juna,
Idan kai sake kurkuku za ka kwana, Ba ka fitowa, a can za ka zauna,
A kan ka qi qauli na noman gyaxa.

Don taimakon kuvutar duniya, Don haka ne aka ce a tsaya,
A noma gyaxa. Jama'a, ku jiya, Tana taimako don a san lafiya,
Ku himmantu jama'a ga noman gyaxa!

Yaqinga ya shafi kowa da kowa, Har ku saraki da ku talakawa,
Mu sa ma wutar ja'irin nan ruwa, Mu roqe shi Allah, mu san afuwa,
Mu sa hankalimmu ga noman gyaxa.

A daina yawan tsegumi da raxa, Da gulma, da hanya ta son yin faxa,
Da sata, da sharri, da yin bankaxa, Ku gargaxi dangi da wannan faxa,

Su qarfafa himma ta noman gyaxa.

Tammat da waqarga don mun taqaita, Malam, karanta wa jama'a su ji ta,
Wanda ya tsara ta ba shi fahinta, Faxa mana sunansa don mu fahinta,
Mu'azu Haxejiya ne, mun faxa.

M. Mu'azu Haxeja, Wudil, 1944

Waqar Gyaxa

Ya Allah ka ba ni basira,
Ka ba ni basira, in waqe gyaxa.

Ku jama'a duk ku karkaxe kunne,
Ku saurari qauli na noman gyaxa.

Sarkimmu na Turai kaza Mr. Churchill,
Suna gargaxi don a noma gyaxa.
Gwamnan Kaduna ku san yayi jawabi,
Yana gargaximmu da noman gyaxa.

Ku san wanga aiki da girma ya ke,
Mu girmama aiki na noman gyaxa.

In ka yi shakka ga girma nasa,
Ka zo ka ga ofis na noman gyaxa.

In ka ga tsarin cikin wanga ofis,
A nan za ka girmama noman gyaxa.

Commander Carror da himma ya ke,
Babban shugabanmu na noman gyaxa.

Jarabar ga ta shafi kowa da kowa,
Mu kori bala'i da noman gyaxa.

Hitler kare, sai mu tasam masa,
Mu harbe shi arne, da noman gyaxa.

Kaico, Japan! Na ga za ki ji kunya,
Za mu buge ki da noman gyaxa.
Aiyururie! Soja sun mana guxa,
Muna taimakonsu da noman gyaxa.

To, ku saraki, da mu talakawa,
Mu xaukaka himma ta noman gyaxa.

Fagen Italy, duk mu kai gudunmawa,
Da harsashinmu na noman gyaxa.

Fagen Burma ma duk mu kai taimako,
Da harsashinmu na noman gyaxa.

Sabon fage ma ba ma bar shi ba,
Mu rarraxe Hitler da noman gyaxa.

Kar mu yi wasa da yin taimako,
Mu taimaki kammu da noman gyaxa.

Riba guda biyu ce za mu samu,
Idan mun yi himma ta noman gyaxa.

Da noman gyaxa za mu samu kuxi,
Mu kori masifa da noman gyaxa.

Alhamdu lillahi n agama waqa,
Da ikonsa na waqe noman gyaxa.

Cikin ofishi na gyaxa ni ka aiki,
Ni, Yakubu Wanka, mawaqin gyaxa.

Yakubu Wanka, da Hassan na Wanka,
Su ne su ka zo don su waqe gyaxa.
Cikin xaki na wayales Kano,
Har can muka je muka waqe gyaxa.

Malam Yakubu da Malam Hassan Bauci, 1944

A gonar Gyaxa na Tono Kekena

Ina ta zame wajibi a gare mu,
Mazammu da mata, mu noma gyaxa.

Ina samari, ku kwana da himma ta aiki.
Ku nuna gwaninta ga aikin gyaxa.

Ina 'yan scout da 'yam makaranta?
Muna son jawabinku, domin gyaxa.

Ina malamai masu aiki a ofis?
Ana raba bonas a gonar gyaxa.

Ina xan haya, mai amanar direba?
Am binne rali a gonar gyaxa.

Ina madugu, madiga, mai fatauci?
Jarinku na can a gonar gyaxa.

Mata na soja, ku xau sungumi,
Ku kai wa mazajenku goron gyaxa.

Ga yadda farashin ya zarce na bara,
Ana so a ninka yawanta, gyaxa.

Saraki da ku tajirai masu kuxi,
Ana so ku taimaki gwamnan gyaxa.

An ce mu huta da aikin kuza,
  Mu koma ga aikimmu, noman gyaxa.
Ya'ya na iska, da ku karuwai,
  Rufi na asirinku noman gyaxa.

Mu daure, mu jure, mu xau anniya,
  Mu san nasara daga noman gyaxa.

Muhammadu Vavura Kano, 1944

Kaya Suna Zuwa, Masu Gyaxa!

Jama'ar birni zuwa qauye,
  Mu karkaxa kunnuwa mu jiya.

Ubammu Bayero na magana,
Yana tsaye, ba bixar inuwa,
  Ishara ce ga mai himma.

Bai tabbata kan kilisai ba,
  "Ina gaishe ku, ya jama'a,
    Ku saurara, ina magana!

Gyaxarku ta bara an gode,
  "Bana kam, an so ku ninka ta da,
    Umurnin mutan Turai.

Mu himmantu, kar mu xau hutu,
  "Ku xaure ciki, ku bar inuwa,
    Ku bauta jikinku kwa huta.

Ku amsa kiran gyaxa gona!"
Bana haja za ta zo da yawa,
  Karammiski zuwa siliki.

An tanadi mai gyaxa, Sarki!
Ku mata, ku bar kishi,
  Ku huxa gyaxa, ku taka sa'a.

Bana mata za ku sha kallo!
Ina 'yan gyatuman qauye,
  Ku xara ruwa cikin buta.

Ku qoqarta zuwa gona,
Ku bi su a hankali da iri,
  Suna sara kuna shuka!

Akwai gwado na zuwa don ku,
Ke saruruwar qauye,
  Zanna ki gani ga sa'a.

Raguwa, mai zuciyar banza!
Dare duk runguma da miji,
  Kya kwana cikin akokonki,

Binanne ba atamfa ba,
Mata na qwarai, a gaishe ku!
  Asubar farko su kan tashi,

Su kan salla cikin gona.

Muhammadu Safiyo, 1944

Gyaxa, yar Churchill

Fa ya Rabbi, ni na yi niyya ta waqa.
  Ga al'amarin nan na shukar gyaxa.

Maraba da ke, 'yar Wazirimmu Churchill.

Maraba da ke, masu iko, gyaxa!

Ku tabbata, naf'inta ya kai salasa,
Ga wanda ya aikata noman gyaxa.

Na farkonsu dai, taimako ne na yaqi,
Ga wannan da ya yi shi, noman gyaxa.

Misalinsa, tamkar kamar ya yi yaqi!
Da Jamus, miyagu, varayin gyaxa!

Kamar na biyunsu, akwai arziki,
Ga wannan da ya yi shi, noman gyaxa.

Ka za na ukunsu fa, murnar amiru,
Ga wannan da ya kama noman gyaxa.

Fa Sarkin Musulmi ya zo har Kano,
"Ina hakimai? Ga jawabin gyaxa.

Fa lalle ku taimaki Sarkin Kano,
Cikin wanga al'amari na gyaxa.

Ku je duk qasarku, ku zam bayyanawa,
Fa kowa da kowa ya shuka gyaxa.
Mu samu mu sha, mu yi noman gyaxa.

Yahaya Sumaila, 1944

Buhun Gyaxa Har Sule Ashirin

Mun gode Allah mai sarauta da'imu,
Ka ba mu laima mai yawa bana, mu yi gyaxa.

Odar farashi tai yawa bana, kun jiya!
Bana Ingilishi sunka qara kuxin gyaxa.

Ina mutane masu qwazo, kun jiya?
Ga mista Karo, mu ce da shi Sarkin gyaxa.

Ku qara gona mai yawa bana ku yi gyaxa.
Ga soja can sun dakace mana ja'iri.

A mu mai da himma, 'yan uwa, kar mu yi sako.
Manyan Sarakunammu sun riqi ja'izi.

Sun kama hanya kan batun noman gyaxa,
Lalle gyaxa asali gare ta na intaha,

Daxinta ya gama duniya, Sarkin gyaxa!

Aliyu A.J Zariya, 1944

Sabuwar Duniya, Gyaxa!

A kowanne daxi mu kutsa mu cim mai,
Mu bar wanda ya yi sake anka tsar mai,

Yana jin takaici mutane su ram mai,
Jawabin gyaxa, bana kowa shi kam mai.
Mu kore talauci da noman gyaxa.
Ku qara wurare, kuna ji, maza!
Gama an rufe mana aikin kuza.

Gyaxa dai mu ke so gare ku, maza,
Mu sami gyaxa mai yawa mu iza!
Soja su san mun tsaya kan gyaxa.

Gyaxa taimako ce, maza, mu yi ta yinta,
Da gaske, mu bar son zama, mu fita.

Mu koma ga daji, mu san kuvuta.
Mutane, ku sa hankali mu yi ta yinta,
Muna kore Jamus da noman gyaxa.

Gyaxa taimako ce fa, don ku sani.
Wurin masu yaqi tana magani.

Batun sa gyaxa bana, sai na gani!
Ga himmar da anka yi nan tun tuni,
Muna bisa niyya ta noman gyaxa.

Mu xauki kulake, mu kore talauci,
Kulakemmu garma, kuna jin kwatanci?

Mu tsira da irli, mu sami mutunci,
Mu zauna cikin ni'ima da abinci,
Idan munka qarfafa noman gyaxa.

Manoma, kuna ji? Ku xau aniya,
Mu sami shiga sabuwar duniya,

Mu share wurare, mu sa gujiya,
Mu sadu da 'yanci, mu san lafiya.
Idan munka qarfafa noman gyaxa.

Isa Gusau, 1944

Gyaxa Alqalin Yaqi

Ku san, tun yaqi bai tashi ba,
Noma shi ke gaba.

Mu sami kuxi mai yawa,
Mu sanya tufafin qawa, takalma 'yan Ikko,
Duk sai domin gyaxa!

Cikin wannan zamani,
Na 'yan tashin hankali,

Da ke son bautad da mu,
Su Nazi, Japan duk haxa,
Mu kai qara gun gyaxa!

Sarakan Nijeriya,
Karo yana gai da ku,

Ya sara yai tsaye,
Yana fara'a kamila,

Can ga manoman gyaxa.

Dabbobi dokarku ce,
Hankaka, mai sakace,

Kurege, Sarkin vula,
Sa gafiya, sa kare,
Kur! Ke kurwar gyaxa!

Amadu Ingawa, 1944

Noman Gyaxa Ya Fi Fatauci

Bushara za ni yi ga maqaryatan nan,
  Masu faxin fatauci ya fi noma.

Wanda ka so ya zauna duniyan nan,
  Cikin sutura, ya sa himma ga noma.

Idan kau ya qiya, a, shi bar gidansu!
  Shi koma can gidan wasu babu girma.

Idan domin tufafi ke fatauci.
  Akwai su cikin qasa, kan kun yi noma.

Mu kama, mu yi da gaske bixar halali,
  Mu sa himma, mutane, mu yi ta noma.

Ina marina, maxinka, ko maqera?
  Bixarku tana ga hannun masu noma.

Ina mabuga, mahauta, masu goro?
  Ku bar kaxa kai na banza, ku yi ta noma.

Talaka, ya kama noma ya yi da gaske,
  Idan kuwa ya qi, ya zama babu girma.

Ku duba man ga nassi har ga sharha!
  Ina kuka sami hujjar raina noma?

Idi Midil ta Bauci, 1944

Sarki Ya Yi Gyaxa, Balle Kai!

Ya xanuwana, dakata mu yi tambaya,
A qasarku can ko ka ji labarin gyaxa?

Mu kam qasarmu, Gwaram, gyaxa ta qarfafa,
Manya da yara duk batunsu sai gyaxa.

Don hakimimmu gida gida duka ya faxa,
Birni da qauye, duk mu sa aniyar gyaxa.
Dagatansa duk ya hallara su wuri xaya,
Yai gargaxi a gare su, don aikin gyaxa.

Yawo ya ke yi shi kaxai, sai ko zagi,
Don gargaxin babban janar, ita ce gyaxa.

Ya gargaxe mu, dare da rana, mu duka,
Don taimakon yaqi, mu sa himmar gyaxa.

Shi kansa yai himmar gyaxa, balle wani,
Gandunsa mil ne, ba ragi, domin gyaxa.

Yaransa su duk sun yi gyaxa, balle wani,
Dagatansa duk gandu gare su na yin gyaxa.

Ya tara 'yam matan gari dukamun gani,
Ya ce da su, "Waqarku sai ta batun gyaxa"

Ya ce da mu, "Zancenku ko a cikin gida,
Ko ku da mata sai ku sa hirar gyaxa.

Mu yanzu kam, yaro idan yai shekara,
Huxu ko biyar, ka ji yana zancen gyaxa.

Babbar janar ita ce gyaxa, duk mun jiya,

Baidai da harsashi guda, qwayar gyaxa.

Kunyar gyaxa daidai da iggwa arba'in,
We ke da wannan taimako? Sai ko gyaxa.

Kowa ya nama gyaxa, watau gindi bakwai,
Ya ba da soja guda, mu sa himmar gyaxa!

Aminu Gwaram, 1944

Sabon Fage Na Kiran Gyaxa!

Ya jama'a, mu xau himma!
Da noma gyaxa ka cin Hitler,

Shaqiyyi xam mutan daji!
Mu xau himma, mu kas daji.

Mu shuka gyaxa, mu san kuxi!
Kwamanda Karo, xan London
Dogo na Gwamna, mai himma.

Ya tara Sarakuna, ya faxi,
"Ku shuka gyaxa, mutan Hausa.

Da iznin Gwamna har Sarki,
Ina roqonku, fadawa!
'Yan kasuwa, ku saurara!

Ina makaxa da 'yam fawa?
Ku daina kixa kuna waqa,

Ku xau garma, mu je gona,
Ingila ta tara qarfinta,
Misirawa sun yi tanyonta.

Su Jamus za a kunyanta,
    Wajen Yamma za a rako ba.
A qare duk su sha kashi.

Muhammadu Daura, 1944

Ba Qwace, Sai Kuxi Hannu

Ga waqa wadda na yi nufi,
    Mu noma gyaxa cikin himma.

Mu kai kanti mu je mu sayar,
Gyaxa, danqo, biyammu a ke,
    Haka ma kuza duk biYamma a ke!

Ba su qwacewa fa don iko,
    Ingilishi masu adalci.

Daxai su ba su yin zalun.
Gyaxa aikinta na da yawa,
    Ana mai don a ba injin.

Dabara kan abincinta,
    Ana yi don a ba soja,

Mazan yaqin fagen fama,
Hitlan nan, bai aboki ne?
    Mussolini ne abokinsa.

Mussolini fa, tasa ta cuslie,
    Ya koma xan hakin doki.

Ban da zagi ba ya cin komai,
Ka ji ranar mai gida Churchill!
    Xan tsoho da ban sha'awa!

Abokin Roosevelt, Churchill,
Na Stalin can qasar Russia!

Kiran nasara su ke ta tafo.
Mun san da zamanku, 'yan ofis!
Ku 'yan sanda, ina taku?

Ku 'yan doka, ina taku?
Mun san aikinku na da yawa,
In kun taso, ku je gona!

Ahmadu Kwangoma, 1944

Gyaxarmu Ta Tafi Burma

A nan ofishin Gaskiya Zariya,
Mun nan da himma kamar ta jiya.

Da saqo ya zo bara, duk mun jiya
Ana so a noma gyaxa duniya,
A sami abin ka da mai son faxa.

Kwamandammu, *Carrow*, da *Lord Swinton*,
Da Sarkin Musulmi, da Sarkin Kano

Da sauran sarkai na *Lord Swinton*,
Da Sarkin Musulmi, da Sarkin Kano.
Da sauran sarakai na *Lord Swinton*,

Nufina sarakan gyaxa kar ku manta.
Sun buxa taron Kano don gyaxa.

Da zancensu ya haxu kan ai ta noma,
Kwamanda ya aiko a nan Editawa,
Yana so a shaida wa dukkan manoma,

Su noma gyaxa wadda ta fi ta kowa,
A xauka a kai Burma, filin faxa.

Baturemmu ya ce, "Ina malamai?
Ku san ba zama, in akwai zalumai!
Mu tashi mu kama a kas zalumai.

Mu jingine fensir, mu xau garmuna.
Mu share fage, yau mu xibga gyaxa,

Noman gyaxa yanzu ya shafi kowa.
Da Sarki, talaka, kaza Editawa.
Mu zare damuttsammu, mu Editawa,

A san ka a nomanta sai mun fi kowa!
Mu bayyana mun so a noma gyaxa".

Baturen ya xau garmuna ya raba,
Ya xauki garma guda ya sava,

Ya duqu ga kunyarsa ba fargaba,
Ya hau ma ciyawa gaba da gaba.
Yana markaxe ta, yana sa gyaxa,

Su Malam Tafida, sarakimmu ke nan,
Na noman gyada, ba awatai a ran nan,

Da ya riqa garmarsa, duk wanda ke nan,
Yana qara qarfi da himma a ran nan.

Uban Ibrahim, Sarkin gyaxa!
Mu juyo ga Malam Imamu, karimi,
Mazan gaskiya, mai darajja, muhimmi.

Yana da fasaha ta komai da komai,

Yana juya garma ta dama da hauni.

Yana nun ya so mu noma gyaxa!
Mu je inda Malam Makama Kano,
Ga aikinsa an san shi har a Rano,

Abeokuta, Ikko, gama har su Barno
Ya xauki garmarsa ya dangano,
Gaban ofishimmu wurin yin gyaxa.

Idan aka cewa ka niyya ga aiki?
Ka ce min da Abdu, da Abdul Maliki,

Da Malam Nuhu, hakaza Ibro, zaki,
Maza masu nuna mutunci ga aiki,
Don ba su latti ga aikin gyaxa.

Cikin lokacimmu mu ke wanga aiki!
Mu kan kama aiki da qarfe shida,

Na safe, mu tashi bakwai da rabi,
Mu je mu mu wanke jikimmu duka.
Mu dawo mu kama rubutun gyaxa.

Ku san mu gyaxarmu a nan Editawa,
Mun ba da kyautarta gun sarakawa,

Domin su aika a kas Jamusawa,
Da Rumanin hakaza Japanawa.
Da albarkacin wanda aiwa gyaxa.

A. Tunau Talatar Mafara, Zariya, 1944

'Yan Arewa Allah Ya yi su masu ilimi da basira a harkokin rayuwa, sadaukai wajen yaqi, adilai a harkar shugabanci masu taimako da barkwanci a hulxa da jama'a. Dubi yadda suka waqe gyaxa suka kuma farkar da jama'ar wajen nomanta cikin hikima, ilimi da fasaha. Munji yadda Arewa ta taimaka wa qasar Ingila da gidunmawar kuxi da kayayyakin aiki iri-iri don a kayar da azzalumai maqiya

adalci da xiyauci. Domin kuwa ai da taimakon gyaxar Arewa ne aka samu galaba da nasara a kan Hitler da abokansa a wannan mummunan yaqi. Kamar yadda M. Aminu Gwaram ya faxi ne a waqarsa ta gyaxa:

Babbar ita ce gyaxa, duk mun jiya,
Daidai da harsashi guda, qwayar gyaxa.

Kunyar gyaxa daidai da iggwa arba'in,
Wa ke da wannan taimako? Sai ko gyaxa.

Kowa ya noma gyaxa, wato gindi bakwai,
Ya ba da soja guda, mu sa himmar gyaxa!

Waxannan baitoci sun bayyana amfanin gyaxa a yankin Hitler. Saboda sojoji da makamantan su duk suna buqatar man gyaxa. Duk wani abinci na soja Kwambis, Kes da da miya da nama duk sai da man gyaxa za a toya su. To idan ba man gyaxa sojoji ba za su sami abinci ba. Idan kuma yunwa ta kama sojojin Ingila da qawayenta, Hitler zai yi nasara ba da wahala ba. A wajen makaman sojoji kuwa daga bindigogi iri-iri da iggwa da tankokin yaqi sai da mai za su yi aiki yadda ake buqata. A wannan lokaci man gyaxa suke sha. Idan kuwa ba a samu ba za a wayi gari ga makamai amma ba su da amfanin komai. Bugu da qari duk inda Ingila ke samun mai ta rasa, sai fa a Nijeriya ta Arewa. Saboda haka ne Sarkin Ingila ya roqi Sarakunan Arewa da su fahimci irin tsaka-mai-wuyar da duniya ta shiga, a kan su taimaka da gyaxa domin a cimma nasara. Sarakuna sun amsa kira sun kuma ceto duniya daga haxarin da za ta faxa!

Yanzu kuma sai mu ji yadda sojojinmu suka fatattaki muggan arna suka kuma tuge saiwar azzaluman duniya. A wannan yaqi 'yan Arewa sun nuna dauriya da jaruntakar yaqi ta inna-naha. Sun taimaka yaya wajen yaqo wa duniya adalci da xiyauci.

Mu Tuna da Sojojinmu

Ko kaxan bai kamata mu manta da sadaukar da rai da nuna jaruntaka da sojojinmu suka nuna a yaqin duniya na Daya da yaqin duniya na Biyu ba. Akwai labaran bajintar sojojinmu iri-iri da jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo ta rubuta akan yaqunan duniya, amma ba kamar yaqin duniya na Biyu. Wakilan wannan jarida kamar Sherif Garba da M. Garba Dikko sun yi qoqarin binciko waxannan labarai daga tsofaffin sojoji waxanda suke ganau ne ba jiyau ba.

Waxannann sojoji abin alfahari ne ga zuriyarsu da qasarsu baki xaya saboda sun nuna bajintar da tarihin jaruntakar yaqi ba zai manta da su ba saboda su ne farko wajen fito da Nijeriya a idon duniya. A wajen nuna jaruntaka kuwa 'yan

Arewa ne kan gaba. A yaqin duniya na Biyu sojojinmu sun gwabza yaqi da Japanawa, waxanda masifarsu, da nacinsu, da jaruntakarsu, da dabarun yaqinsu da qarfin makamansu sun fi na sojojin Veitnam waxanda suka addabi Turawan Amurka suka kuma gagaresu, duk da qarfin qasar Amurka.

Kamar yadda 'yan Vietnam suka zarana sojojin Amurka haka sojojinmu suka razana Japanawa suka kuma karya su a yaqin duniya na biyu. Irin tarkunan da suke kafawa da kuma miyagun dabarun yaqi iri-iri da Japanawa suka nuna tare da yaqin sunquru, duk basu hana sojojinmu nuna wa Japanawa su mazaje ne ba. Jamusawa da abokanta sun sha kashi a hannun sojojinmu.

Kada ku manta Arewa ce kan gaba wajen fidda Ingila kunya a wannan yaqin da ya kusa ya gagareta da ita da qawayenta. Jamusawa na da qarfi da suka haxu da Japanawa sai suka haxa qarfi da qarfe, amma sai 'yan Arewa suka nuna wa duniyu su maza tuwon qaya miyar allura ne. Saboda haka sai suka yanke wa qasar Jamus kaba a yaqin duniya na Biyu, wato sun maimaita jaruntakarsu na yaqin duniya na farko.

Tun a wajen horon soja da koyon harbi aka fara tsinkewa da 'yan Arewa. Da aka gama basu horo a wurare da garuruwa daban-daban, sai aka turasu wannan yaqi, inda suka yi ficewajen baiwa kura nama. A wannan yaqi ne sojojinmu suka nuna bajinta a yaqin da suka gwabza a Indiya da Burma da sauran qasashen da Japanawa da Jamusawa suka mamaye.

Sojojinmu sun sauka a qasar Indiya, inda suka yi ta artabu da Japanawa. A labarin da wani jarumin soja, mai suna Habibu ya bayar, wanda shi ganau ne, labarine wanda yake xauke da jaruntakar 'yan Arewa mai daraja ta xaya. Shi wannan sojan Ganabtir ne, wato mai aiki da iggwa ya kuma qware wajen harbi, inda ya sami qarin girma ya zama fulkofur, wato soja ma igiya biyu kafin ya tafi wajen yaqi. Ya ce a Indiya sun shiga wani gari da ake kira Bombay daga nan suka tafi garin Kalandan. A wannan gari ne suka fara qwamawa da Japanawa, Habibu ya ce:

Kafin mu qetare kogin Kalandan kuwa, sai da akayi kare jini biri jini. A lokacin nan ne Baqar Fata suka zama sarakai, komai muqamin Bature sai ya zama talaka domin kuwa dukkansu saboda son rai da yawan kasala da son yin sarauta, sun kasa wucewa gaban yaqi sam. A nan ne mu 'yan Igwa da muka ga abin zai vaci, sai muka yi qunar baqin wake, muka cije muka shiga gaban yaqi. Domin kuwa in muka yi sakaci, a wannan lokaci duk cikinmu ba za a sami ma wanda zai kai labari ba. Kuma bugu da qari ma, muka qulla a ranmu sai mun rama irin varnar da Japanawa suka yi mana.

A nan mun yi ta gwabza yaqi ba ji ba gani. Kai! A taqaice dai da qarfi da yaji muka qwace garin Kalanda daga hannun Japanawa, su

kuma Japanawan suka gudu filin kau. To, saboda ganin mun qwato wannan gari mutanen Japan sun ji tsoro qwarai da gaske. Daga nan sai muka keta wata hanya ta tsakiyar daji muka dawo da baya. A wannan hanyar mun yi ta fama da Japanawa qwarai da gaske. Daga nan ba mu zame ko ina ba sai garin nan Ciningan, a nan ne kuma mu sojojin Nijeriya muka taru bayan kuwa a da muna warwatse ne kawai a cikin dajin Allah. To, Malam ka san yadda sha'anin xan-Adam gajiyayye ne, a nan ne fa tsananin son iskar duniya ya zo mana saboda haka sai muma muka fara karaya. A lokacin nan ma wasu kuka su ke yi da hawaye su dai a dawo da su gida.

Bayan wata shida a Ciningan mun qaru da dabarun yaqi sosai. Sai muka koma gwabza yaqi a karo na biyu. A dai-dai wannan lokaci ne sojojinmu suka yi Babban Baqo.

Yaqi cimar maza. Ana cikin tsakiyar gwabza wannan yaqi ne sai Turawa suka lura da jaruntakar 'yan Arewa na raguwa a fagen yaqi. Da yawa daga cikinsu ma har sun razge suna varkewa da kuka suna roqon a dawo dasu gida. Turawa na ganin wannan abu fa, sai suka ji tsoron kada Ingila ta sha kashi a wannan yaqi saboda 'yan Arewa ne jaruman yaqinta, da sune take murqushe Jamusawa da abokanta. To, ga 'yan Arewa sun razge. Me ya kamata ayi?

Turawa sun san muhimmacin Sarakuna, su ne sinadarin 'yan Arewa, saboda haka sai suka shaida masu abubuwan da ke faruwa a fagen gaqi. Suka kuma ba da shawarwari da a tura wani Sarki fagen fama don ya yiwa sojoji qaimi domin su qara himmasu ci gaba da nuna jarunta abin da aka sansu da shi ba tsoro ko ragwanta ba.

A wajen zaven Sarkin da zai tafi wajen yaqin sai kara ya faxa a kan Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo. An zave shi ne saboda mahaifinsa Sarkin Katsina Muhammadu Dikko, sadauki ne kuma jarumi ne mai daraja ta xaya. Xansa kuma magajinsa Sarki Usman Nagogo ya samu Tarbiyya da horo a wajen sa. Saboda hake ne gwamnatin Jihar Arewa ta tura wannan mashahurin Sarki zuwa fagen yaqi.

Sarkin Katsina a Fagen Yaqi

An yi Taron Sarakunan Arewa na musamman a Kaduna wanda aka yi a ran 22 ga Mayu shekarar 1944. Wannan taro yana da muhimmanci sosai. Saboda an kira wannan taro ne don Sarakuna su aikawa sojojinmu da ke wajen yaqi saqon alheri da su kara qwazo da himmatuwa a wajen yaqi.[1] An tura Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo qasar Hindu don ya sadu da sojojinmu ya qwarzanta su. A dalilin

[1] GTK 10 ga Mayu, 1944, shafi na 4

haka ne Sarakunan Arewa kuma suka yi taro na musamman akan so Jan Ragamar Nijeriya a yaqin Hitler, da kuma yadda za a xauki matakan durkake shi.

Kafin wannan ranar taro kuwa, Razdantai sun yi taronsu a garin Jos, a wannan lokaci har suka qara wa Sarakuna shawarwari daga cikin abubuwan da za su tattauna. Ga su: (1) Ko za a sake kafa daffo inda 'yan Doka za su je koyon aiki? (2) Ko za a kafa makaranta, inda malaman ofis na En'e za su koyi aiki? Kuma a wannan taro za a kawo hanyar da za a bi don a qwarzanta sojojinmu da ke fagen yaqi. A lokacin da Sarakuna ke taro a Kaduna wani lokaci su kan yi a zauren taro na kwalejin Kaduna daga shekarar 1938. Amma a shekarar 1941 sai suka bar taruwa a wannan kwaleji saboda an baiwa soja aron wurin, sai a shekarar 1944 sa'an nan ne Sarakuna suka komo da taronsu a wannan kwaleji ta da, na wani xan lokaci. A taronsu na shekarar 1944 yana da muhimmanci sosai, saboda haka ne aka gayyaci wasu Sarakuna daga Kudu don su halarci taron. Saboda haka sai wannan taro ya zama na qasa baki qaya.

A cikin waxanda za su sa wa shawarwarinsu tubarraki kuwa har da manyan Sarakuna uku daga Nijeriya ta Kudu. Waxannan Sarakuna su ne; da Oni na Ife, da Alake na Abeokuta da Oba na Benin. Saboda muhimmanci wannan taro, sai aka xauki bayanai da jawaban da aka yi a faifan garmaho wanda za a aikawa sojojinmu da ke qasar Hindu. Duk Sarakunan da suka halarci wannan taro an yi faifan garmaho don Sarakuna su aikawa da sojojinmu a Burma da gaisuwa. Wato, in sun yi jawabinsu sai a xauka a faifai akai shi qasar Hindu.[1] Waxannan jawabanne ake nuna wa sojoji ta sinima a Bataliyoyi da Kamfanonin sojojinmu don a Kwarzantasu.

Ana so sojojinmu da ke fagen yaqin Hitler su riqa jin saqo ta gaisuwa da addu'a daga Sarakunan Arewa. Saboda soja na jin daxin haka don yana qwarzanta da himmatuwa wajen nuna juriya da bajintar yaqi, idan yaji muryar Sarakuna na albarkarsa, a wannan lokaci na yaqi cimar maza! Saboda haka taron Sarakuna yana da muhimmaci masu yawa. Duk taron da Sarakuna ke yi yana muhimmanci ga ci gaban Arewa da jama'arta. Duk da cewa babu wani wajen taro isasshe. Amma ba a samu wajen taro takamaimai ba sai da aka gina Gidan Shawara.

Sarakunan Arewa sun zavi Sarkin da ya dace da yin wannan ziyara, ya je qasar Hindu ya gano sojammu da ke can suna yaqi. Ita ma Majalisar Yaqi ta Afirka ta Yamma sai ta yi na'am da wannan zavi saboda Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo ya gaji mahaifinsa ta hali da aiki wanda kowa ya san shahararren jarumi ne. Sarki Dikko ya shahara ga yaqi.

Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo ya tafi Kano, inda har ya ziyarci makarantar koyon shari'a, ya kuma baiwa xaliban wannan makaranta sadakar fam biyar. Ya sa du da Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayaro wanda ya yi bankwana

[1] GTK 10 ga Mayu, 1944 shafi na 6

da shi, ya kuma yi masa addu'ar Allah ya dawo da shi lafiya. Ya tashi cikin jirgin sama tare da wani hafsa na soja mai suna Manjo Mackray da Malam Isa Kaita wanda ya raka shi.

A cikin wannan muhimmiyar ziyara, gwamnatin qasar Hindu ce zata xauki baquntarsa har ya taso. A Delhi babban birnin qasar Hindu zai sauka wurin Sarkin Yaqi H.U Richards, C.B.E. Da ma abokinsa ne sun saba tun sa'ad da Richards ya ke aikin soja a Nijeriya. Sarkin zai yi kamar mako biyar a wannan tafiya. Zai kewaya wurare da yawa. Zai tafi birnin Calcutta da Birnin Bombay har Arakan zai shiga inda runduna ta 'yan Afirka ta Yamma ta fara karo da Japanawa. Zai kewaya dukan sojan Nijeriya. Saboda haka wannan ziyara da Sarkin zai kai ba mai sauqi ce ba.

Da Sarkin Katsina ya tashi daga Nijeriya zuwa Hindu ta Masar ya bi, cikin jirgin sama tare da Sakatarensa M. Isa Kaita, inda har ya ziyarci Masallacin Muhammadu Ali a Masar. Ga shi nan, ga shi nan har ya isa Delhi. A wannan birnin ne ya iske Janar Warell, Wakilin Sarkin Ingila a wannan qasa. A wannan rana da shi suka ci abincin rana. A nan kuma Sarki ya iske Janar Auchinleck, wanda ya ke xaya daga cikin Sarakunan yaqin Ingilishi na Gabas. Shi ne ma ya baiwa Sarkin masauki. A ranar da Janar Auchinleck ya kira Sarkin Katsina dina, a can ya sadu da tsohon abokinsa Janar Richards, Kwamandan Delhi. Sun san juna tun Richards yana birgediya a Zariya.

Sarkin Katsina ya yi yawo qwarai a cikin birnin Delhi, ya ga manyan wurare irin wanda jama'a ke girmamawa. A wannan lokaci ne har ya kai ziyara wani tsohon Masallacin Juma'a wanda a wancan lokacin shekararsa arbaminya da ginawa. Abin ka da malami, Sarki Usumanu na ganin wani Alqur'ani wanda aka rubuta shi da wani tsohon rubutu, sai ya xauko yana karantawa M. Isa Kaita. Wannan abu ya baiwa limamin masallacin, wanda ya zo tarbarsa mamaki ainun, da yaga yana karatu da kuma qira'a mai kyau. Tilas ya natsu!

Sarkin Katsina zai yi tafiya mai nisa a cikin kasar Hindu da Arakan yana zaga sojammu. Abin ka da sadauki haka ya riqa yin wannan tafiya, wata sa'a bisa jirgin sama, wata sa'a bisa na qasa wata sa'a bi sa mota.[1] Tafiya yake yana saduwa da jama'a iri-iri a wurare daban-daban, ba tare da nuna alamar gajiya ko lalaci ba. A wannan ziyara ya na nuna kwarjini da muhibba, duk inda ya tafi, sai jama'a ke varkowa ta ko'ina suna maraba da Sarki.

Maraba Da Sarki

Inda duk Sarki Usumanu ya sa qafa, sai sojammu ke varkowa kamar za su haxiye shi saboda murna. A ran 9 ga Oktoba 1944, ya tashi daga birnin Delhi ya nufi wani sansani, inda ake qara wa Sojan Afirka ta Tamma dabarun yaqi. Kafin

[1] GTK ta 124, 8/11/1944

ya tashi, ya yi godiya ga Wakilin Sarkin Ingila da sarakan yaqin Gabas, waxanda suka yi masa xawainiya.

Abu ya zo daidai, sa'ad da ya ziyarci Hindu, a wannan lokaci ne sojammu ke sake wani yunquri a fagen Arakan. A wannan lokaci ne kuma aka rivanya yawan Sojan Afirka ta Yamma waxanda ke fagen Burma domin sun fi waxanda suka yi Yaqin Kamaru da Is'Afirka a wancan babban yaqi sau da yawa. Saboda a wannan yaqi, gurgura ba ta cinsa, sai an tashi baki xaya an haxiye Japan, tana ji tana gani. A haxiye su a yaqin teku, a haxiye su a yaqin qasa a kuma haxiye su a na sama! A cikin wannan yunquri ne Sarkin ya zo ya qwarzanta Sojan Afirka ta Yamma, zuwan na sa kuma ya yi tasiri mai kyau.

A duk inda ya shiga a qasar Hindu, lokacin sallah baya wuce shi. Don ko'ina ya je in lokacin sallah ya yi Sarki Usumanu ke shigewa gaba ya yiwa soja sallah. An ce a cikin sojan Nijeriya waxanda ke Hindu da Burma akwai Katsinawa da yawa, sojoji Musulmi duk sun nuna farin ciki da zuwansa har ma su kan zo su faxi gabansa, su cire huluna, su ce ya shafa kansu su sami albarka.[1]

Sarkin ya kan ziyarci asibitoci don ya duba marasa lafiya da masu rauni. Ran nan da Sarkin Katsina ya je wani asibitin Soja, yana duba waxanda aka yi wa rauni yana kewaya su gado-gado, karaf sai ga Abdu Shinkafi xam bargarsa. Duk rabonsa da bargar Sarkin Katsina bai fi wata huxu ba. Shi ke nan sai suka shiga taxin gida. Abdu na tambayar dawakin Sarkin waxanda ya sani. Da ma raunin nasa kima ne a wajen fuska.[2]

Gwamnatin Jihar Arewa ta taimaka da ta tura Sarkin Katsina Usman Nagogo zuwa Indiya don ya qara wa sojojinmu qwarin gwiwa da himmatuwa wajen cimma manufa. Ya kuma je a dai-dai lokacin da tsoro da fargaba ke damun sojojinmu a fagen fama. Domin a wannan lokaci ne sojojin suka yi gwabzawar farko da askarawan Japan, inda suka yiwa sojojinmu mummunan varna.

Ganin haka fa sai tsoro ya kama sojojin, jini kuma ya zo musu akaifa, da yawa daga ciki suka firgita don tsoro. Har wasu ma suka varke da kuka sharaf-sharaf, suna roqon a maido su gida ba su son su halaka. Fargaba asarar namiji. To, ana cikin wannan mummunan hali ne sai Allah Ya kawo masu Sarkin Katsina wanda ya zo takanas don ya qara musu qarfin gwiwa, ya yaba wa qoqarinsu ya kuma isar da saqon 'yan Nijeriya musamman 'yan Arewa, na nasara da fatan Allah Ya dawo da su gida lafiya, cikin nasara don su zama abin alfahari ga qasarsu.

A daidai wannan lokaci ne Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo ya yi wa dakarun yaqi jawabi don su himmatu tare da mayar da hankali wajen tuge azzalumai maqiya zaman lafiya a duniya. Sarkin ya ce wa sojojin muna alfahari

---

[1] GTK ta 124, 8/11/1944

[2] *Ibid*.

da ku a cikin wani jawabi da ke qarfafa gwiwa da sanya alfahari, ga jawabin kamar haka:

"Hausawa suna da wani karin magana, su kan ce, "zuwa da kai ya fi saqo." Don haka, da izinin Gwamnati, da na manyan Turawan soja, da na Sarkin Musulmi, da na sauran 'yan'uwanmu, na zo da kaina in gaishe ku, saboda aikin da ku ke sha, don ku, da nufinmu, da na dukan jama'a na duniya, masu son zama lafiya. Safiya da maraice, muna ta yi muku addu'a, Allah Ya ba ku nasara bisa ga abokan gabar Sarkin Ingila, waxanda suka hana duniya zama lafiya. Kullum muna fata, Allah Ya maido ku gida lafiya, ku ci gaba da zama lafiya, ku tarar da ni'imomi waxanda ku ka haqura da su, ku ka zo nan, don ku yi taimako wajen turmuje maqiyanmu.

"Sarkin Musulmi na Sakkwato, da Sarakuna, da matanku, da iyalanku, da sauran jama'a duka na gida, sun a gaishe ku da kyau. Kullum muna murna mu ji labarin bajintarku da tsare aikinku sosai. Idan mun karanta labarinku cikin jaridu na duniya, ko muka ji a cikin wayar iska, mu kan ji daxi qwarai. Lalle muna alfahari da ku. Kun isa 'ya'ya!

"Buqatarmu ku qara himma da kulawa ga aikinku, ku samo ma qasashenmu suna, da daraja madauwamiya, a cikin qabilu na duniya. Don wata rana, a riqa cewa mu ma da mu aka murje Jamusawa da Japanawa, maqiya 'yan-Adam.

"Da ma asalinku 'ya'yan mayaqa ne. Kakanninku sun san yaqi, kuma jarumai ne balle a ce ga wani azzalumi ya abka muku.

"Kuma muna so mu tuna da ku, sojan Afirka ta Yamma (West Africa), waxanda aka sa yin waxansu ayyuka a bayan fagen fama. Aikinku da na masu buga wuta duka xaya ne! Muna yin gaisuwa musamman ga masu yin ayyukan xaukan kaya, da masu isar da soja da buqatunsu. Ba don taimakonku ba, da sojanmu a fagen fama ba su iya ci gaba da faxa ba.

"Mun sani sarai irin halin Japanawa. Abokan gaba ne muggai marasa imani. Mun sani kuna faxa a cikin mawuyaciyar qasa, wadda take cike da cuce-cuce. Mu kan karanta duk wannan a cikin jaridunmu, masu faxa muku qashin gaskiya. Muna gode wa likitocin soja, masu jiyyarku in ba ku da lafiya, ko an yi muku rauni. Muna gode wa masu yin hidimar abincinku. A gida, muna maida himma mu yi qoqari wurin taimakon yaqi.

"Na gani da kaina ana kula da ku a nan Hindu. Hafsoshinku suna kulawa da ku. Na wakilci dukanku, na gode wa babban Kwamanda, Lord Louis

Mountbatten, da janar George Giffard, Kwamandanku, da dukan hafsoshinsu da su ke kula da ku haka.

"Amincin dake tsakanin qasashenmu da mulkin Sarkin Ingila mai qarfi ne qwarai. Muna alfarmar zama cikin mulkin nan. Lokacin da duniya take zaune lafiya Uwarmu qasar Ingila, tana yim iyakar qoqarinta, don ci gaban qasashenmu da kuma qaruwar arziqin 'ya'yanmu."[1]

Malam Xanshuwa wani jarumin soja ya bada labarin irin gwagwarmayar da suka yi a garuruwa dabam daban. Danshuwa ya ce daga garin Macina suka shiga jirgin ruwa mai suna "Shillings ", daga nan suka tafi garin Calculta. Daga wannan gari suka ta fi Tansiga, amma a garin Poana ne suka saxu da Sarkin Katsina. Da ma Turawa sun shaida masu cewa za su tarar da wani Sarki wanda ya zo daga Nijeriya ta Arewa. Xanshuwa ya ce, "Haba Malam! Kada ka tona irin murnar da muka yi a ranan nan, wato jin haka da muka yi sai tamkar an ce ga mu rannan a gidajenmu ne sai murna baki har kunne!

Sarkin Katsina ya qwarzanta sojoji a garuruwan da ya je da kuma labarin zuwansa fagen yaqi ma sai ya zama abin alhairi ne da kuma alfahari ga dukkan sojojin Nijeriya musamman 'yan Arewa. Wannan jarumi ya bayar da labarin haxuwarsu da suka yi da wannan mashahurin Sarki, inda ya ce:

Da saukarsa da wani mutum, sai aka tara mu duka, ya yi mana jawabi, inda ya ce sun zo ne musamman saboda am ba su labarin irin qoqarin da mu keyi a wajen yaqi saboda haka takanas suka niqo gari don su ganmu, mutanen Nijeriya kuma suna gode mana. Suna fata kuma za mu qara daurewa bisa qoqarin nan namu wanda aka sammu da shi, kuma suna fata Ubangiji Allah Ya mayar da da mu gidajenmu lafiya.[2]

Bayan Sarkin Katsina ya gama yi masu jawabi sai kuma ya shiga ya duba barikin waxannan sojoji ya kuma ziyarci wuraren ban sha'awa a wannan gari duk inda kuma yaje jama'a sai murna suke yi suna qara farin ciki. Jim kaxan bayan ziyarar Sarkin Katsina a fagen yaqi, a shekarar 1944, sai Allah Ya kawo qarshen wannan mummunan yaqi. 'Yan Arewa sun karya lagon maqiya! Jamus sun xaga tutar tuba. Saboda haka ziyarar Sarkin Katsina tayi tasiri sosai.

Wannan Sarki shi ma sai ya nuna jaruntaka domin a filin yaqi ya same su, a lokacin da suke shirin karon barta da askarawan Japan. Wannan zuwan ya taimaka wa sojojin qwarai da gaske. Tun da yaje ya yi masu addu'a ya kuma sa masu albarka, ba a qara jin sojojin sun nuna tsoro ko lalaci ba. Daga nasara sai

---

[1] GTK ta 124, 8 ga Nuwamba 1944, shafi na 5

[2] *Ibid*., shafi na 4

nasara suka riqa samu. Ga abin da jarumi Abdu Lakwaja ya ce: "A wannan lokaci ne sojojinmu suka shiga wani qungurmin daji wanda a cikinsa akwai manya-manyan duwatsu waxanda na tabbata babu irunsu a Nijeriya da qasar Kamaru, sa'an nan kuma a gindin su ga ruwa ya kai ya komo. A duk duwatsun da muka hau, babu Mai girma da tsawon wannan dutse, wanda ake kira "dutsen fai-fai. "

Jarumi Habibu shi ma ya ce: "Ba za mu manta da ranar da za mu hau kan wannnan dutse ba don a ran nan ne Mai girma Sarkin Katsina tare da marigayi Abdulqadir Makama (Allah Ya gafarta masa), suka ziyarce mu. Wannan ziyara ta faranta mana rai qwarai kuma ta qara mana wani sabon karsashi. A lokacin da suka zo sai muka ga kamar muna gida ne. Kafin su tashi sun yi mana addu'a da huxuba. Allah kuma ya karvi addu'arsu don a wannan rana ne mu ka ci wani gari wai shi birnin Maition muka qwace daga hannun Japanawa. "

An yi wani qazamin karo a wani qauye wai shi Haila mil biyar daga birnin Dawazare saboda ganin varnar da Japanawa suke yi mana sai nan da nan qungiyar Bataliya ta Huxu ta karvi gaba. Saboda qwazon wannan bataliya har sojoji suke yiwa bataliyar wani kirari suna cewa, "Bataliya Maza Waje. " A nan ne ma na ga abin mamaki wato saboda tsananin yaqi, har ma Turawa ba su qaunar a ce da su Turawa. Sai ka ga Bature ya shafe fuskarsa da baqin gawayi wai don ya zama kamar Baqin Fata. Japanawa ba wanda suke jin tsoro da shayi kamar Baqin Fata qwarai da gaske.

A Bataliya ta Huxu sam babu Ibo ko xaya, sai Gwado-gwado, da Munci da Hausawa saboda jaruntaka. Amma da abin ya yi qamari sai kuma mu qungiyar masu Igwa, muka shiga muka saki wuta kamar ruwa.[1]

An ce sai an gwada a kan san na qwarai.Wannan yaqi ya qara fito da jaruntakar 'yan Arewa, da qwarewa wajen yaqi tare da jurewa wuya da wahala wajen cimma manufa. Idan dawa ya vaci sai a nemo sojojinmu domin su mazaje ne ba mazare ba!

A cikin wannan yaqi ba jaruntaka sojojinmu suka nuna ba har da fasaha. A wani yaqin da aka qara gwabzawa da Japanawa, sai aka harbi wani sojanmu a kafaxa, amma sai abokinsa mai suna Lawal Kano ya cire masa harsashin da ya kafe a kafaxarsa ba tare da vata lokaci ba. Jarumi Habibu ya ce sunan sojan da aka harba Abdu Kano. An cire harsashin a kafaxarsa kamar yadda likita zai cire. Wannan cire dalmar da ya yi ne ma Likitan Sojoji ya yaba masa. Daga nan sai sojojinmu suka zo inda aka yi wa sojojin Gwalkwas wato Ghana qofar rago, inda suka shiga wani mugun wajen da Japanawa suka kewaye su za su halakasu. Jarumi Habibu ya ci gaba da ba da labarin cewa:

---

[1] GTK 2 ga Nuwamba 1962, shafi na 12

"A nan sai da aka yi aiki na kwana huxu don a lokacin Japanawa sun shirya lallai kawai sai sun ci sojojin Gwalkwas ko da tsiya ko da arziqi. Sai aka sa kamfanin Turawa zalla kuma suna da Igwa goma sha-bakwai, duka suka shirya, mu kuma Baqar Fata muna da Igwa guda goma. Da muka shirya da misalin qarfe 8:30 am na safe, sai kawai muka fara buga wuta tun daga kamfanin mu ba don a san ga mu nan tafe ba, a xan tsakanin lokacin nan ba ka jin komai sai amon iggwa. A taqaice dai a wurin yaqin nan, sai da muka kai qarfe 3:30 am na wata safiyar.

"A nan fa da Japanawa suka ga dai abin ba dama, sai suka aika don a kawo musu taimako daga hedkwatarsu. Da aikawarsu kuwa sai ga motoci wajen saba'in dukansu kuwa cike da sojoji. A cikin motocin nan guda saba'in sai guda xaya kawai muka samu muka rushe ta da iggwa, su duka babu xayan da ya qaras da abin da ya auku sun mutu. Mun kwana uku a nan muna ta gwabza yaqi sa'an nan mutanen Gwalkwas waxanda musamman ma saboda a qwato su ne aka shiga wannan yaqin, suka samu xan kafa suka kuvuta daga Japanawa, har ma an harbi burgediyan su a qafa. Da muka ga haka, sai muka aika Jirgin Saman Likita ya zo ya kwashe waxanda aka yi wa rauni. Jirgin saman likita guda goma musamman suka je don kwasan masu rauni."[1]

Bayan da aka kuvutadda sojojin Gwalkwas, sai godiya su ke yiwa sojojin Niijeriya, suna cewa ai ba domin su ba da Japanawa sun kashe su duka ba sauran ko xaya. A nan wurin sai aka umurci sojojin Gwalkwas da su koma baya, dawa ya vaci! A yinin wannan rana masu godiya na yi, amma su Japanawa kuwa suna cike da hushi da neman xaukar fansa. Saboda haka sai suka xana wa sojojinmu talala, su na bin su suna kai musu farmaki. Har a wata gwabzawa da a ka yi wani Bature ya zautu:

A ran nan ne wani Bature mai anini biyu ya faxo cikin raminmu yana kuka, wai shi Japanawa za su vata masu lokaci. Abin haushi ma shi ne, wai ashe shi wannan Baturen ya yi sabon aure ne ya qosa ya koma gida ya ga sabuwar amaryarsa, shi ya sa yake cewa wai Japanawa za su vata masa lokaci. A bin da ya bamu haushi ko tankawa da shi babu wanda ya yi, shi kuwa duk inda ya tafi sai ya yi ta faxin haka wai shi dai "vata lokaci. "[2]

Ranar 11 ga watan Fabrairu yaqi ya turnuqe a wajen fagen Arakan a Burma. Nan soJan Ragamar Nijeriya suka fara karo da Japanawa a kwarin Kaladan. Da farko Japanawa sun soma tsayayya, amma yanzu suna nan sai korarsu sojojinmu

---

1 GTK 2 ga Nuwamba 1962,

2 *Ibid*., shafi na 9

ke yi, suna nan sun bi Kogin Kaladan tsaye. Amma kafin su kai kogin, sai da suka wahala cikin wani qungurmin jeji. Su hau wannan dutse, su gangara wannan kwazazzabo, suna saran kurmi, suna yi wa motocinsu hanya don a riqa biyo su da kayan faxa da abinci. Wurin ba a taba tsammani wani zai yi qarfin hali ya zo da mota ba. Amma duk da haka sojojinmu sai da suka yi shi, har ya zama abin yabo. Saboda keta wannan kurmin daji da mota ya baiwa kwamandojin sojoji mamaki matuqar gaske. Kuma keta wannan jeji mai haxarin gaske nuna jarunta ne tsagwaranta. Da sojojinmu suka keta wannan kungurmin dajin sai suka yi gadaje, suka sa su a ruwa kamar jirage, suna bin kogi da su. Wallahi, wannan abin al'ajabi ne, babu kuma wanda ya tava tunanin akwai sojojin da za su saida ransu, wajen shiga wannan kurmi da bin wannan Kogi, a wannan lokaci mai haxarin gaske.

Yamma da sojojinmu kuwa, sojan Ingilishi na faxa da maqiya wajen dutsen Mayu. Sojojinmu na Yamma da dutsen, arnan Japan suna Gabas, kowanne yana qoqarin ya qetare dutsen nan ya kori wani. A haka nan kuma waxansu jarumawan Ingilishi suka vulla Gabas da dutsen, suka nufi Japanawa. Ba sai Japanawa suka tura waxansu sojansu su bi daji su katse musu hanyar gida ba! Duk da haka mutanenmu ba su razana ba, suka ci gaba da aiki. Wannan jaruntaka da suka yi ta qayatar da kowa. 'Yanuwansu Ingilishi suna qoqari su ture Japanawa, su kawo musu gudunmawa. [1]

Churchill ya Gode wa Sojan Ragamar Nijeriya

Sojojinmu sun nuna gayar jaruntaka, an yamutsa sojan Japanawa wajen Dutsen Mayu, waxanda suka yi niyyar su katse rundunarmu su farma Hindu. Cikin yaqin nan kuwa sojan Afirka ta Yamma da sauran sojan Runduna ta 14 duk sun gwada jaruntaka. Har Waziri Churchill wato Firayim Ministan Ingila da bakinsa ya aika ya yaba su, ya ce: "Mun gode muku da kuka hargitsa Japanawa a yaqin nan na kurmi, wanda su ke tsammani ba mai iya cinsu gare shi. Kun karye musu ahuri, kuma kuzarin da suke yi da, yanzu ya yi sanyi. "

Sojojinmu da ke bin kogin Kaladan suka yi karon battar Amore da arnan Japan wajen Rafin Pichaung. Ran 25 ga Fabrairun shekarar 1944 dai suka yunqura suka tura su Yamma, suke qetare rafin suka ciwo qauyen Kyauktaw. Suna nan yanzu suna ci gaba qarqashin tuddai Yammacin qauyen, maqiya kuwa na qoqarin cijewa.[2]

Ashe waxansu sojan Afirka ta Yamma suna wajen fagen Arakan suna gwabzawa. Suna cikin waxanda suka riqe Dutsen Mayu sai da aka yamutse sojan Japanawa tukuna. 'Yan Arewa sun fatattaki Japanawa sun tarwatsa su, sun kuma

---

[1] GTK 17.8. 1962, shafi na 9

[2] *Ibid*, ta 107, 15 ga Maris 1944, shafi na 2

shiga kurmi suna farautar sauran maqiya da suka warwatse cikin jeji kamar 'ya'yan iska.

Tun can da ma sai da aka koyawa sojojinmu yadda za su kaura da Japanawa, don an san sun iya yaqi cikin qurmi kwarai, kuma ga iya kwanto. Shi yasa da dai suka haxu da Japanawa su ke bisa. Sojojinmu sun sami horo mai kyau wajen harbi da bindiga da igwa, sun kuma qware wajen yin kwanto da samame, sun kuma nuna jarunta da juriya a duk lokacin da suke gwabzawa da Japanawa.

Ran 6 ga Fabrairu 1944, Baturen wata jarida ya ba da labarin irin samamen da sojojinmu ke yi wajen Arakan. Ran nan sojojinmu suka tafi samame daga Maungdaw daddare, Turawa ma sai da suka shafawa fuskokinsu baqin fenti, sai ka rantse da Allah baqar fata ce! Suka shiga jirgi irin na masu fito, suka bi kogi. Ko filafilai ma sai da aka lulluve su da tsumma, wai kada aji motsinsu. Can sai suka sauka cikin wata fadamar shinkafa su ka shiga maci sulululu! Kamar ruwan yaci su mutum yana ji yana gani ko tari ya zo sai ya haxiye, don kada maqiya su ji su. Da suka kai kusa da maqiya, sai waxansu suka tafi da rarrafe zuwa wurinsu, don su gane yadda suke ciki, sauran kuma na can suna makyarkyatar xari cikin gandun shinkafa. Ran nan aka tarar ashe lallai maqiya a wurin sun fi qarfin a faxa musu, sai kawai aka ja jiki baya aka kai labari. Baturen nan sai faxi yake shi dai ba ya son ya sake irin wannan samame! Amma ga sojan nan namu sun yi irinsa har sau xari da saba'in da uku (173).[1]

Duk inda sojojinmu suka shiga, Japanawa sai suka riqa nemansu ido rufe don su hallaka su, don neman fansa amma sai sojojinmu suka vace masu a surquqin dajin Burma. Amma duk da haka Japanawa sun rutsa sojojinmu. A surquqin dajin Burma Japanawa suka rutsa sojojinmu. A lokacin kuma ana tsala ruwan sama kamar da bakin qwarya kuma da tsakar dare. A dajin Burma kai malam ai dajin Burma babu irin abin da mutum zai faxa maka game da wannan wuri, don abin ya wuce a faxi sai ka gani kawai. A cikin ruwan nan haka waxansu suka yi ta haqa rami suna shiga.

A wannan daren ana ruwa, wuri ya yi duhu qwarai ga iska mai sanyin tsiya, sa'an nan kuma ga sararin sama ma bai yi garau ba don akwai hadari, ai sai ganyaye kawai kake ji suna wani irin qara kamar usir, sai ka ji dajin ya xauka fii! fii! Da dare ya tsala sai sojojinmu suka riqa jin ana kiran sunayen su amma ba wanda ya amsa, kowa ya yi lamo a cikin raminsa. Da gari ya waye suka fito, sai sojojinmu suka yi ta dariya saboda irin kiraye-kirayen da suka ji cikin dare kuma sojoji sai kwaikwayonsu su ke yi. A nan kuma aka ce za a yi mana wani xan abin tunawa waton don mu karya kalace.

Jin haka sai muka sake, kowa ya shiga harka gwargwadon ikonsa, waxansu suna ta aski, waxansu kuwa suna ta yin salla su kuku kuma suna can suna ta yin

[1] GTK ta 107, 15 ga Maris 1944, shafi na 2

girki. To, ashe hayaqin nan da ke tashi daga sanwar kuku zai jawo masu tsiya, don saboda hangen hayaqin nan ne sai Japanawa suka gane inda suke sosai, saboda haka ba su yi aune ba sai suka ji saukar iggwa, sai kuma mai ruwa ta biyo ta a baya. Kai, kafin ka ce kwabo wuri ya yamutse! A wannan cikin ruxami sai suka fa rasa yadda za su yi, sai nan da nan suka xuru a cikin rami, aka ce masu kada kowa ya yi harbi koda sau xaya ne.

Mutanen fa suka riqa aiko masu da wuta kamar ruwa abin ba dama. Su suna tsammani a haka za su tsaya, sai can kuma ga jirgin samansu ya zo ya duba ya wuce. A dawowa ta biyu sai ya jeho masu bom qwarara guda uku, da ya sake zagowa na uku kuma, sai ya sako masu iggwa mai ruwa, kai abin dai gwanin bantsoro na qasa ba su daina harbi ba, ga jiragen sama suna ta sako masu iyayen harbi daga sama. Amma kuma wani taimakon Ubangiji, duka harbin nan da jirgin saman Japanawa suka yi ta zubo masu daga sama, babu xaya daga cikin mutanenmu da ya mutu ko ya ji ciwo, dalili kuwa shi dai jirgin nan bai san inda suke katamamme ba, shi dai yana zubo wane kawai da ka, ko kuma direban jirgin ya sha giya ne ya bugu ko oho![1]

Irin wannan kuskuren ya kan faru a wajen yaqi. Wani lokacin xokin samun nasara kan haifar da mummunan nadama. Allah ne ya tsare sojojinmu da hayaqin abincin da kuku ke dafawa ya jawo masu halaka gaba xaya. Yaqi da Japanawa ya fi wuya da asarar rayuwa saboda jaruntakarsu da makaman yaqi. Yaqi ne kuma da ya fi qarfin faxar baki, domin duk yadda soja ya kai da ba da labarin wuyarsa, bai faxi komai ba sai dai ya bada kanunsa kawai.

A wannan yaqin, dubu sun vata, dubu sun kashe kansu saboda masifar wahala, an kuma kashe dubu. Amma a cikin wannan baqar wuya da sojojojin Turawan Ingilishi suka nuna gazawarsu a zahiri, a wannan hali ne 'yan Arewa suka nuna su jarumawa ne waxanda duniya ta yiwa jinjina, sun kuma samu kyauta da yabo iri-iri kuma masu yawa. Abokan gaba sun sake dabarar yaqi. Japanawa sun koma voyewa a bisa itatuwan kwakwa.

Da sojojin Japanawa suka lura sojoji Baqar Fata na masu kisan kiyashi in sun yi arangama da su, sai suka riqa hawa kan itatuwan kwakwa suna voyewa, wani lokaci daga nan suke harbin sojojinmu. A wani lokaci kuma tarko iri-iri suke xanawa a qasa kamar haqa babban rami cike da mashi masu tsini a baibaye da ciyayi. Idan sojoji suka faxa ramin su halaka. Wani lokaci kuma rassan itatuwa ke faxowa kan sojoji, waxanda suke da masu da ke da tsini. Sojojinmu sun ga dabarun yaqi wajen abokan gabansu, amma duk da haka ba su hana su ci gaba ba. A duk inda aka ritsa su sai su nuna bajinta wadda ba wanda ya tava ganin irinta.

Amma da dai suka gane sojojin Japanawa a bisa itacen kwakwa suke, sai kawai muka riqa zuba wuta a dukkan itatuwan kwakwan da muka gani, ai fa

1 GTK 17/8/1962, shafi na 9

malam a lokacin nan ko ba ka yi awo ba, in dai har ka yi harbi, a cikin duhun itacen kwakwa, sai kawai ka ga mutum ya suvuto yana ihu da shure-shure zai mutu. Amma a bisa haqiqanin gaskiya kafin mutanenmu su fahimci cewa Japanawa a sama suke sun yi mana varna qwarai da gaske. To, amma da muka gane lallai mun yi ramuwar tsiya a wurin. To, da haka fa muka yi ta gwagwarmaya da su har mu ka isa wani gari wai shi Tambaza.

Bayan mun xan shaqata a Tambaza muka tashi kuma muka ci gaba da tafiya, a lokacin nan jirgin sama ba shi da dama ya kawo mana abinci don yana gilmawa a sararin sama Japanawa suna harbinsa, saboda haka sai ya zamana, ko za a kawo mana abinci a kan hanya, sai dai a zubo a bisa waxansu irin alfadarai na Indiya. A nan ne naga abin kunya da Turawan Ingilishi su ka yi, wato a ran nan munyi wani xan karo da arnan Japan wanda yake bai kai na awa huxu ba, amma aka kashe Ingilishi biyar. To, da sauran suka ga haka, sai suka shiga shafa baqin tukunya a fuska wai don su zama kamar baqar fata. Da na tambayi wani bature na ce "me ya sa ya shafa datti a fuskarsa, sai ya ce mini, ai wai sun fi mu baqin jini a wajen Japanawa don sun ce su ne suka kawo mu muke ta kashe su.

Mu na cikin tafiya mu na kuma yin yaqi kaxan-kaxan sai muka iso wani wuri da sojojinmu suka sawa suna "Dutsen Mai Saje. " A nan ne muka kwana takwas muna buga wuta. Shi Mai Saje wani sojan Japan ne mai masifar tsiya, wato shirin hanyar mugunta wurin wannan arne, abin har ya vaci. Don babu irin wahalar da bai gwadawa sojoji ba, kafin a gane haimci da dabararsa. Lokacin da muka fahimci hanyar muguntarsa, ya gamu da masu dabara harda ta banza, ai sai da muka kama shi domin a lokacin da mutanensa suka ga abin ba na yi ba ne, su ka ga lallai wuta ta ishesu sosai, sai suka fara gudu.

Kashegari da muka wuce sai muka kwana a wani tudu daga nan sai muka tashi muka sauka a wani xan qauyen Bamis. A wannan qauye a kwai gidaje gudu huxu, da saukarmu sai aka ce Bataliya ta Biyar ta yi gaba da mil xaya, su ka yi gaba suna sakin waya ta qasa inda sauka. Ashe akwai sojojin Japanawa a wurin. Sai Japanawa suka bari sai da sojojinmu sun tuve suna haqa ramuka, sai kawai suka faxa masu, to, su gasu basu shirya ba. To, a bayansu xin kuwa akwai wutsiyar teku kuma ya kawo ruwa. Wato an ritsa sojojinmu ke nan.

Ganin haka sai nan da nan aka buga mana wayar nan ta qasa, aka ce kamfanin farko su tafi don su yi taimako. To, kafin wannan kamfani su kawo taimako, a kwai wani soja wanda ake kiransa Yaro Zuru, kai, shi wannan soja ya shirya kansa sosai, don shi kaxai ne ya hana sojojin Japan su farwa qungiya ta farko, wato da ya riqe Barinzan, in sun yi kukan kura za su faxo masu, sai ya mayar da su baya, abin mamaki ma wato ni dai kam ban tava ganin mutum da shiri-irin wannan ba. In ka dubi irin bom wanda ake jefo shi da su, ai abin sai ya baka mamaki. Amma Malam wallahi, ko an jefo xin sai ta qi fashewa. Sai shi kuma ya xauka ya jefo su da shi, sai ya fashe ya yi ta hallaka Japanawa. Ni dai ban da

wannan ina tsammani sojan nan yana da kau da bara, don duk harbin bindiga da ake masa bata yin komai da shi.[1]

An daxe ana labarin wannan jarumin soja da aka ce sunansa Yaro Zuru, yana xaya daga cikin sojojin da suka nuna bajintar jarunta a lokacin yaqin duniya na biyu babu kamarsa. Akwai sojoji 'yan Arewa da yawa da suka ba duniya mamaki. duniya kuma ta yi masu godiya da jinjina.

A wani labarin kuma jarumi Habibu Mulki ya ce, ya ga wani abin mamaki, a inda wani Soja Gwado-Gwado ya tafi xauko xan'uwansa da Japanawa suka harba. A wannan lokaci kawai Japanawa suka shiga zuba wa mutumin nan harsashi amma abin mamaki shi ne, ga harsashi ya huhhuda rigarsa, amma bai tava fatar jikinsa ba. Da haka suna harbinsa har ya xauko sojan da aka raunata. Yana dawowa sai Turawa suka kewaye shi suna ta duba jikinsa. Suka fa dame shi da ya tafi wajen likita ya duba shi, ya bashi magani mai yiwuwa an yi masa rauni. Da dai suka dame shi, sai ya ce da su ba zai tafi ba, don kuwa ba a ji masa ciwo ko xaya ba. Ai daga nan, sai Turawa suka riqa kiransa "Mutum Mai Juju. " A wannan karon, sojojin Japan da aka kashe ba su qidayuwa, ko'ina ka duba sai gawarwakinsu kawai za ka gani a kwance kamar fari.[2]

Sojoji suka ci gaba da tafiya sai da suka isa wani waje inda Birgediyan sojojin Gwalkwas yake. Shi ne ya basu labarin cewa kwana goma sha-uku ke nan, suna fafatawa da Japanawa. Saboda sun sami wani rami a wata fadama da suka shiga, duk wanda ya leqa wannan ramin tasa taqare ke nan. Da isowar sojojinmu wannan waje, sai Birgediyan ya ce zai tashi ya ci gaba, amma Baturen Bataliya ta Goma ya ce masa ya tsaya saboda wannan wuri yana da haxari sosai Japanawa sun vuya sosai, a wajen tudunnai suka kewaya wannan waje, sojojin kuma sun voye a ramukan waxannan tudunnai saboda haka ko anyi harbi, a banza baya samunsu. Kai kuwa kana leqawa sai ka ji an haxo ka da dalma.

A wannan waje sai da sojojinmu suka kwana shida suna qulle-qulle da shirye-shiryen yadda za su ci wannan mugun wuri. To, a rana ta bakwai, sai Baturen Bataliya ta goma ya faxi cewa gobe da safe kowa da kowa ya fito wajen yaqi, babu kuku ko boyi, kowa zai xauki bindiga don za a yi yaqin duka wato *General Attack* wanda ko da tsiya ko da arziqi, sai an ci Japanawa a wannan waje.

To, abinka da qarar kwana, bayan ya ba da wannan doka, sai ya tafi shi kaxai don ya leqa ya ga yadda Japanawa suke, da Odalensa ma zai biyo shi, sai ya ce ya koma shi kaxai za shi. Leqawarsa ke da wuya, sai ga wani sojan zai wuce, bai yi wata-wata ba sai ya sa bindigarsa ya danqara masa harbi ya faxi. Xan uwan

---

[1] GTK 17 ga Agusta 1962, shafi na 9

[2] *Ibid*. 10 ga Agusta 1962, shafi na 9 : mu tuna da sojojinmu. Garba Dikko ya Xauko labarin

wannan ya zo don ya xauke shi, shi ma sai ya harbe shi. Ashe, wani sojan Japan daga sama da bindigarsa ya hango shi, sai kawai ya yi wa Baturen nan fashi da harsashi a hanci, ai fa nan take ya faxi a tsakiyar tudun.

To, a nan ne fa aka rasa wanda zai je ya xauko gawarsa. Sai Turawa suka cewani saje ya je ya xauko shi. A nan sai sojoji Baqaqen Fata suka ce sun qi, sai dai Turawa suje su xauko shi domin idan soja baqar Fata ya mutu, su ne su ke zuwa su xauko shi, saboda haka kowa ya riqa xauko nasa. A nan Turawa su Keftin da su Manjo da sauransu suka tsaya jako-jako suka fa rasa na yi, don kowa ya san haxarin wannan waje. A nan dai wani Bature ya yi ta maza ya kwanta ya ja ciki har ya kai wurin ya sa hannu ya jawo shi. Nan da nan sai aka yi waya jirgin sama ya zo ya xauki gawarsa, aka naxa wani Sabon Manjo ya riqe Bataliyar.[1]

Sojojinmu sun ji zafin wannan rashi da suka yi saboda haka sai suka harzuqa sosai. Nan da nan sai aka aiko jiragen sama xauke da durom-durom na fetir suna jefawa a wuraren da Japanawa suke voyewa, sai fetir ya warwatsu a wurare daban-daban. Japanawa ba su san fetir ba ne saboda haka kafin su ankara sai jiragen sama suka biyo da bama-bamai, nan da nan sai wuta ta tashi ko'ina. Mafi yawancin Japanawa sun qone qurmus, an kuma kashe wasu da yawa.[2]

Kowa ya yaba wa sojojinmu da suka yi yaqin Burma da sauran garuruwa, saboda jaruntakar da suka nuna wajen sadaukar da rayukansu don duniya ta kuvuta daga makircin Japanawa da iyayen gijinsu Jamusawa, sun tsaya samun lambar jaruntaka. Abin ya zama kamar gasa, kowanne sai qoqari yake, yana neman abin da zai yi a ce masa 'madalla'. A wannan lokaci ne ma aka yi wa wasu sojojinmu jinjina aka kuma basu lambar *Military Medal*. Ita wannan lambar yabo ta jarunta irinta kowannensu ke zakwaxin samu har abin ya zama gasa.

Tarihin yaqin duniya na Biyu ba zai manta da Musa Kwango ba, wanda yana xaya daga cikin waxanda suka sami wannan muhimmiyar kyauta. Akwai soja mai lamba 38863 mai suna Kofir Adamu Gafasa da N.A. 27478 mai suna Saje Ali Yola. Kowannensu ya nuna irin tasa karamar, don na baya su huta. Kowanne yana ganin arnan Japan na vararrako wuta, bai nemi mavoya domin ya tsirar da ransa ba. Sai kawai ya fuskanci abokan gaba, yana daka wa mutanensa tsawa su maida bugu. A wurinsu, farin cikinmu ya ma fi lafiyarsu. Duk sojan da ya kansance haka kuwa, to ya cancanci a yi masa sakamako da wannan lamba ta girma.[3] Ita wannan lambar ta *Military Medal* tana da muhimmancin gaske.

Sojan Arewa a wannan yaqi sun nuna jaruntaka domin duk hautsinin da aka yi a Kohima, cikin qasar Hindu, bai razana su ba har sai da suka kori Japanawa.

---

1 GTK, 10 ga Agusta, 1962, shafi na 9

2 *Ibid*, 14 ga Agusta, 1962, shafi na 8

3 *Ibid*. Ta 122, 11 ga Oktoba 1944

Birgediya Richards shi ne shugaba kuma abokin Sarkin Katsina Usuman Nagogo, wanda shi ma ya zo fage yaqin takanas don ya yi wa 'yan Arewa qaimi a kan su dage su tabbatar da cewa an kai ga nasara a wajen wannan yaqi da zalunci. Wannan Birgediya ya san 'yan Arewa sosai, saboda haka da su ya yi amfani wajen tarwatsa garkuwar Japanawa a Birnin Kohima, inda Japanawa suka riqa zuwa kamar gwano, ba kuma irin dabara da muguntar da ba su gwada ba, amma Richards ya qi saki. Ta haka har aka naxe Japanawa daga hanyar da ke tsakanin Birnin Imphal da Kohima kamar tabarma, kora ta miqa ta yi Kudu.[1] Ruguntsumin da aka yi a wannan yaqi tare da bajintar da mutanenmu suka nuna ya cika wani falle na tarihin wannan yaqi.

Shi Birgediya Richards (wanda ya zama Janar daga bisani) ba baqon 'yan Arewa ba ne, domin shi ne shugaban *Brigade* na Zariya. Zamansa a Arewa da kuma hulxarsa da 'yan Arewa sun taimake shi gaya wajen cin nasara a fagensa na yaqi, har ya kai ga likkafarsa ta yi gaba, ya zama Janar. Shi kam ya yi sa'a. Amma Manjo Cartwright wanda ya daxe a Kano shi ne Baturen 'Yan Mairuwa, kuma ya shahara qwarai da gaske wajen qwallon dawaki, sai ya rasa ransa a yaqin Burma. Shi ma ya kai muqamin Birgediya kafin ya mutu.[2] Gumurzun da aka yi a wannan yaqi da kuma nasarorin da aka samu sun sanya Sarkin yaqin Ingila yi wa sojojin Nijeriya ta Arewa jinjina da godiya ta san barka.

Mountabatten ya Gode wa Sojojinmu

Janar Mountabatten, Sarkin Yaqin qasar Ingila wajen Burma, ya yi godiya da jinjina qwarai ga sojojinmu da sauran sojan Runduna ta 14, da suka kori Japanawa daga qasar Hindu a wajen Kohima. Ya ce:

"Tun bara war haka, da Japanawa suka kore mu daga Gabas, ba su sake yin xauki mai qarfi ba kamar wannan na fagen Kohimi da Imphal. Ga shi kuna tarbe su, har kuwa kun fatattaka mini su. Da Japanawa sun yi nasara, da ba mu da sauran hanya ta kai gudunmawa ga 'yan'uwammu, waxanda suka izo Japanawa daga Arewa. Amma wanda duk bai zo ya ga wannan wuri da kuke ba, da yadda yake da damina, ba zai san irin aikin bajinta da kuka yi ba."[3]

An yi qazamin faxa sosai, lokacin da Japanawa suka ritsa Ingilishi a Imphal. Ko abinci sai daga sama ake jefo musu! Gudunmawa kuwa, sai a xebo sojan Hindu daga fagen Arakan cikin jiragen sama, a zo da su shuu, a saukar da su cikin Imphal. Amma duk da haka abin ya faskara. A wannan lokaci ne na qaqa-ni-kayi,

---

1 GTK ta 112, 11 ga Oktoba 1944

2 *Ibid.*

3 *Ibid*., 5 ga Yuli, 1944, shafi na 2

sai da 'yan Arewa suka zo suka karya lagon maqiya. Tun daga wannan lokaci ne sai kadarin jamusawa ya karye.

A wannan lokaci ne aka yi wa sojajin Ingilishi mummunar rutsawa, za a kuma yi masu kisan kiyashi. Abinci dai, ko da yake ana sako musu, bai wadace su ba. Abin da mutum ya saba ci a rana guda, sai a ba shi rabinsa! Haka suka zauna har wata biyu, sai daga baya da bajintar sojojinmu aka buxe hanyar Kohima, kana aka kuvutadda sojan Ingilishi.[1] Yaqi cimar maza! Don haka ne Janar Mountabatten na Burma ya yi godiya tare da yin jinjina ga sojojinmu. Saboda sun qwato jama'arsa daga kisan kiyashi.

To, 'yan Arewa ga ranar ku dawa ya yi dameji, yaqi cimar maza! An kira su su ceto sojan Ingilishi, sun amsa kira basu kuma ba da kunya ba. Irin wannan godiyar nuna bajintar da Janar Mountabatten na Burma ya yi wa sojojinmu xaya ce daga cikin xari. Jaruntakar da soja 'yan Arewa suka nuna a wannan yaqi ne ya taimaka gaya wajen kawo qarshensa, ya kuma baiwa qasar Ingila nasara a kan jamusawa da abokanta.

An daxe ana yaba wa jaruntakar 'yan Arewa a yaqin Burma. Wani jarumin soja mai lamba N.A.72022, mai suna Saje Garba Kukawa ya ce, "Wata rana da muka yi wani wawan gwabzo da arnan Japan, har kunnuwanmu sai da suka xume saboda tsananin qarar bindiga." Ya qara da cewa, "A wannan rana ne muka harbe jiragen abokan gaba har guda hamsin!"[2] Sojojin 'yan Arewa da yawa sun sami lambar *Military Medal* domin nuna tsagwaron jaruntaka. Yaqin Burma ya yi suna sosai har waqa aka yi masa.

Waqar Burma

Fa bismillahi na fara waqa,
Za ni fa waqar samarin Burma,

Ina soja soja, ina boyi boyi?
Ina kuku kuku, mutanen kicin?

Ina su akawu? Kirawo min su tica,
Da ku za mu waqen batun ga na Burma.

Akwai wata rana Baturen wurimmu,

---

[1] GTK ta 5 ga Yuli 1944, shafi na 2.

[2] *Ibid* ,Ta 125, 22/11/1944

Ya tara mu Nazik, qasa ce ta Burma,

Bayan kwana kaxan munka tashi,
Sai ga mu a daji, qasa ce ta Burma.

Fa kowa da kowa yana haqa rami,
A domin fa tsoron bayaqinsu arna.

Cikin dajin fa ba shan sigari,
Fa dominsu arna, mutane na Burma.

A nan fa qur ta farko ta kaure,
Afirka suna yanke arna a banza.

Jini na gudu, sai ke ce su Kubanni,
Sunan wani rafi a Birnin Zariya.

Su kuku su kawo su biskit su ba mu,
Da kwambis fa, shi ne abincimmu Burma.

Gawa a wurin nan fa ta fi a qirga,
Ta arna, mutanen qasar Japanawa.

Yini xaya tak, sai ga Mondo a hannu,
An kore iyalin janar xin Japanawa.

Watammu guda munka tashi ga Mondo,
Muna so mu kai can garin Japanawa.

Akwai wani dutse a can a garin nan,
Dutsen nan fa shi ne mavoyarsu, arna.

In sojan qasa ne kai, ka ga ta kanka,
Ka hau shi kana yin salati, a Burma.

Idan ka yi sauri ka faxo ka karye,
Im ba karaya, sai mu xauke ka gawa!

Muna gangarowa, sai ga mu a Kalapanzin,
Sunan wani birnin qasarsu ta Burma.

A nan fa qura da qura ta kaure,
Ganan gobe sai wanda Allah ya sa!

A nan fa Bahaushen mutum yai halinsa,
Yana kwaxa waqa, yana kashe arna!

Muna yin kirari da sunansa Allah,
Muna yanke kansu, mutan Japanawa.

Ga abinci, amma babu damar ka ci shi,
In ka tuna yadd ka ke kashe arna.

In Keftin ya shirya, sai ya ce muku "Faya!"
Tum, fum, rum ka ke ji, a kan kafirawa!

Watammu guda shida sur, babu qari,
Muna qone arnan qasar, Japanawa.

Watan nan guda shida, ran da sunka qare,
Sai babban janar ximmu ya zo gare mu.

Yana mana murna da yaz zo gare mu,
Yana mana godiyar kashe arna.

A yanzu muna nan wurimmu na farko,
Muna kwance a daji na Burma.

Fa mu ne iyalan Janar Katarayit,
Mutanen Recce, ba mu son Japanawa.

Janar Katarayit, ubammu na farko,
Da munka rasa a qasar Japanawa.

Fa na qare waqar qasar Japanawa,
Ta'ala ka taimaki kowa da kowa.

100760 *School Master*, Garba Zariya, 1944.

Sarkin Katsina ya Dawo Daga Hindu

Ran Laraba 22 ga Nuwamba 1944 da qarfe goma sha biyu da rabi, ran nan Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo ya sauka Birnin Kano daga qasar Indiya. Ya iske Razdan da Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayaro, da Ciroman Kano, da Madaki da Wali duk sun hallara. Daga Katsina kuma ga Waziri, ga Wali, ga Kankiya, ga Sarkin Musawa, ga Sarkin Sulluvawa, ga Makama ga Galadiman Asibiti. Kano ta cika maqil da manyan mutane masu tarben Sarki, a filin jirgin sama. Zuwa can sai ga jirgin sama buu ya sauka.

A lokacin da jirgi ya ja birki sai duk idanun jama'a suka koma wajen jirgi. Can sai ga Alhaji Usman Nagogo ya kunno kai yana hamdala ya dawo lafiya kuma ga manyan mutane sun yi dafifi wajen tarbensa. Sarkin Kano da Razdan suka tarye shi, suka gaisa. Daga nan sauran jama'a suka bi suna gaishe shi. Manjo Mackray wanda aka sa ya raka shi, sai ya dubi mutanen Katsina, ya ce, "Ga Sarki nan na maido muku!"[1]

Duk shagalin taryen Sarki da Alhaji Abubakar Imam Editan Gaskiya aka yi. Ciroman Kano Alhaji Muhammadu Sunusi ne ma ya xauki baquntarsa, a kuma cikin motarsa suka yi yawon taryen wannan Sarki. Bayan an baro filin jirgin sama an nufo gari, sai Sarkin Kano ya ce, "Editor, ga labari zan gaya maka, ka ba ni goro! Alqali yana nan yana fama da wata shari'a ta wani saurayi. Shi saurayin sai ya yi hayar keke, ya tafi kasuwa ya yi sayayya. Daga nan sai ya ce zai je ya kawo kuxin, amma ga basukurinsa zai bari a rumfa kafin ya dawo. Shi ke nan sai ya wuce da kayan da ya saya, ya tafi ke nan! In 'yan haya sun ga basukur ya vata, sai su bazu har cikin cikin qasa suna bixa. Suna nan suna nema sai su ji basukur ya fito daga kasuwa, sai a bar mai basukur da shari'a da mai hajja. Haka ya auku sau da dama, har abin ya dami alqali, sai kwanan nan aka kama saurayin. Ana nan ana qara binciken maganar"[2]

Duk waxanda suka ji wannan labari da Sarki ya basu sai suka yi mamakin wannan irin sabuwar dabara ta zamba. Sai Walin Kano ya ce, "In an gama shari'ar, sai a yi shela, don mutane duk su lura da irin haka a gaba". Sarki ya ce,

---

[1] GTK ta 126, 6 ga Disamba 1944

[2] *Ibid.*

"su dai 'yan haya, suna da hali mai kyau na taimakon juna. Im basukurin guda ya vata, duk sai su hau su bi hanyoyi ko'ina su taimaki xanuwansu bixa. Abin da kuma ake so ke nan mutane su riqa gama kai suna taimakon juna".[1]

Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayaro mutum ne mai ilimi, hikima da basira. Ya bada wannan labari ne domin ya yi kira ga jama'arsa su yi koyi da halin 'yan haya wajen taimakon juna wato matsalar mutum guda ta zama matsalar al'ummarsa baki xaya. Da taimakekeniya da juna ne al'umma ke ci gaba. A kullum Sarakunan mu suka yi magana sai ka ganta wa'azi mai ma'ana da amfani ga rayuwar duniya da lahira.

Daga filin jirgin sama ba a zame ba sai gidan Razdan na Kano. Aka zauna aka shiga taxi. Sarkin Katsina ya ce, "Soja kam sun yi murna da ganina qwarai. Kuma Sarakunansu na yaqi suna yabonsu da gaske! Ni ma na yi murna da na sami damar zuwa na gansu. Sun ce a gaida musu da mutanen gida. Na zo da saqo da yawa nasu, zuwa ga mutanensu. Har ma ga xan qunshin kaya wani ya ce a kawo wa alqalin Kano".

Razdan ya ce, "Yaya abinci?" Sarki ya ce, "Ai abinci ya wadace su. Duk sun yi qiba. Shinkafa dai, kullum sai sun bar ta." Sarkin Kano ya ce, "Daga ina kuka taso yau?" Sarkin Katsina ya ce. "Daga Junaina. Watau jiya muka baro Masar" Sarkin Kano ya ce, "Ka ga mu kuwa da muka taso daga Masar, cikin jirgin ruwa da na qasa, sai da muka yi kwana uku kana muka iso Kahartum!"[2] Daga nan sai Razdan ya je ya kama waya, ya sanad da gwamnan Kaduna Sarkin Katsina ya sauka lafiya. Sarkin Katsina kuma ya je ya kama waya, suka yi gaisuwa da shi.

Abubuwan da Soja ke so a Burma

Ya dawo aka kuma ci gaba da gaisuwa. Razdan ya ce. "Akwai wani abu wanda suka gaya maka ya dame su?" Sarki ya ce, "I, akwai abubuwa uku da su ke kukansu. Guda dai rashin goro. Mutanen Kudu su kuwa rashin asawaki. Na gaya musu, in na zo zam faxa a yi shawara a gani, in zai yiwu a riqa kai musu goron. Amma na bayyana musu wuyar jirage da kuma halin goro, wurin saurin lalacewa.

"Abu na biyu kuma, rashin samun takardu. Amma dai babban abin da su ke kukanga shi ne rashin samun lifi zuwa gida. Akwai waxanda suka yi shekara biyu, har uku, har da mai huxu rabonsa da gida. Irinsu su ne waxanda daga Nijeriya sai aka kai su koyo a sauran qasashen Afirka ta Yamma. Daga can, bayan sun yi kamar shekara guda, sai aka nufi da su Hindu.

"Da na ji haka, na bayyana musu wahalar yaqi. Na ce im ba an shirya ba, in sun cira qafa, duk inda suka ci, abonkan gaba za su qwace ke nan. Aiki ya

---

[1] GTK, Ta 126, 6 ga Disamba 1944.

[2] *Ibid*.

koma baya! Na ce duk da haka, in na zo zan sanad da ku, a yi qoqarin yadda za a taimake su, in yana yiwuwa".[1]

Daga nan Razdan ya ce, "To, me ya fi ba ka mamaki a can Hindu?" ya ce, "Irin gininsu yana da ban mamaki! In ka gani sai ka ce ba xan Adam ya yi ba." M. Abubakar Imam ya ce tun da na ji haka a bakin Sarkin Katsina na san lalle mutanen Hindu sun isa a yaba musu. Domin kuwa zuwansa Ingila biyar, ya ga gine-gine irin na Turawa, ya ga irin na Larabawa, amma duk da haka ka ji yana yaba na Hindu, ai ka san da magana!

Sai daga baya M. Abubakar Imam ya sami labari gun M. Isa ya ce ai sun je har Tajmahal. Ka kuwa san Tajmahal, waxansu suna cewa duk duniyan nan, ba ginin da ya kai shi kyau. Har ma ana sanya shi cikin manyan abubuwan da su ka fi ba da mamaki a duniya. Da za a watse daga gidan Razdan, sai aka yi shawarar yadda za a shirya wa Sarki lokaci, ya je ya yi magana da jama'ar Kano a Wayar Iska. Da aka taso, sai gari!

Da la'asar, sai M. Abubakar Imam suka koma gidan Sarkin Katsina tare da Ciroma, ya je ya kai Sarkin Katsina gidan Wayar Iska ta Kano. A nan suka iske shugaban wurin, M. Bello Xandago, ya shirya wa Sarki ya yi magana da jama'ar Kano. Can kusan magariba, muka zo gidan Sarkin Kano. Sarkin Kano da na Katsina suka shiga suka gaisa. Daga baya kuma sai ga Razdan ya iske su. Da suka qare gaisuwa aka mai da Sarkin Katsina masauki. Su Editor kuma, aka je masauki aka yi magariba, aka dawo hira gidan Sarkin Katsina.

Kafin mu ba ku labarin nan, mun ga ya kamata ku san yadda Editor Abubakar Imam ya ke a Katsina. Ko da ya ke a Kagara aka haife shi, shi a Katsina ya girma, can ya yi makaranta, tun daga Elementare har Kolej, har ya yi malanta shekara biyar a can, duk qarqashin en'e ta Katsina. Daga can ne aka kawo shi nan, da za a fara Gaskiya. Ya saba da Sarkin Katsina na yanzu, don sun zauna makaranta tare, kuma tare su ke qwallon doki. Har wa yau kuma, shi Editor, da shi ne Sakataren hakiman Katsina gun shawara, kuma shi ne ma'ajin farko ga jam'iyyar Katsina. Shekararsa kusan ashirin a can. Yanzu ma, duk danginsa da gidajensu, suna Katsina. Ka ga ashe a fadar Katsina shi xanuwa ne. To, saboda haka, da na koma masaukin Sarkin Katsina da dare, na yi gaisuwa, sai na zauna aka ci gaba da hira tare da ni.

Hira Da M. Isa Kaita

Da aka jima, sai na koma waje na iske abokina, M. Isa. Muka shiga taxi. Ya ce, "Kai, Imam, soja sun yi murna da suka ga Sarki cikin kayansa. Ashe da sun yi zato da kaki za mu je. Domin kuwa, ka san oda ce, kowa sai da kaki ya ke

[1] GTK, Ta 126, 6 ga Disamba 1944.

zuwa qetaren ruwa. Amma da suka ga Sarki da rawani, da alkyabba, suka ce sai suka ji kamar sun koma gida". Na tambaye shi me ya ga alama sojammu sun qaru da shi? Ya ce, "Zumunci" Duk sun zama 'yanuwan juna. Ba mai cewa shin a Nijeriya ne ko na Golkwas, ko na Saliyo ko na Gambiya. A'a, kowannensu ka tambaya daga ina ya ke? Sai ya ce daga Afirka ta Yamma.

Muka dai ci gaba, na tambaye shi ba wani haxari da ya auka musu? Ya ce, "Babu, ba haxari, ba ciwo! Sai dai mun kuru wata rana. Wata rana ce, ran Jumma'a, muka kwana a wani wuri. Bayan mun bar wurin, Jumma'a na kewayowa, sai Japanawa suka kawo hari bisa wurin, har suka sassaki bom!" Na ce batun goro, ku kun je da na cinku ne? M. Isa ya ce, "I, Sarki ya je da goron ci. Kuma da ka ji ya cewa Razdan soja na bukatar goro, shi da kansa har ya ba da (£100), ya ce a saya a jarraba kai musu a gani. Turawan nan na soja sun yi wa Sarki abubuwan girmamawa qwarai. Ka ga in za a tafi wani wuri, sai a sa soja, Turawa, su hau babur, da bindigogi, su wuce gaba, don gudun haxari. In kuma Sarki ya sauka, sai a sa Turawa da bindigogi, su yi ta sintiri qofar masaukin, suna gadi, har gari ya waye!"

"Kuma shi wannan Bature Manjo Mackray, wanda aka sa ya raka mu, na kirki ne qwarai. Ya xauki kansa kamar bara ne na Sarki. Ni da shi kuwa kamar abokai. Ai Sarkin Katsina na yabonsa gaya!"

"Shi kuwa wannan Bature Manjo Mackray, wanda aka say a raka mu, na kirki ne qwarai. Ya xauki kansa kamar bara ne na Sarki. Ni da shi kamar abokai. Ai Sarkin Katsina na yabonsa gaya!"

Har wa yau M. Isa ya ce, "A maganar Gaskiya Ta Fi Kwabo soja sun ce 500 a ke kai musu, ta yi musu kaxan. Abin da su ke so kamar 2,000. Batavuren da ya raka mu ya ce in mun dawo zai yi magana."

Imam, ya yi Gaisuwarsu ta 'Yan Gida!

Can da aka watse daga hira a waje, Sarkin Katsina ya shiga gida, muna shirin komawa masauki, sai ga jakadiya, ta ce. "Ina M. Imam? Sarki na kira ciki!" Na tashi na bi ta har qofar xakinsa. Na yi gaisuwa, muka zauna mu biyu muka yi ta hira. Na yi ta tambayar duk abin da na ke so.

Sarki ya ce, "Lalle, ashe Gwamna wuya ya ke sha, in ya zo kewayar qasa. To, misali ya taso daga Ikko, in ya zo Ilori, sai ya iske Sarkin Ilori ya shirya abubuwa ba iyaka, duk kuwa yana so ya nuna masa. Da safe ya wuto Bida, ya iske Sarkin Nufe shi ma ya shirya haka, Sarkin Zazzau, Kano, kana ya iso Katsina! Nan kuma mu ce sai ya kewaya duk ofisoshi, da Yamma mu ce sai ya je kallon qwallo. Kowannemmu, ba ya tambayar irin abin da Gwamna ya yi jiya. Kowa dai, abin da ya shirya lalle a gani, a gani kuwa duka. To, misali irinta aka yi mini.

"Yadda abin ya ke, kamar misali ka sauka Zariya, sai a ce maka da safe za ku Katsina ku duba soja, sa'an nan ku wuce Sakkwato, janar Wane na jiranku, tare za ku yi kalaci. In kun tashi daga nan, za ku ci abincin rana a Kwantagora, za ku ci na dare a Mina, ku yi kallon sinima a Kaduna. Ku dawo Zariya, nan ne masaukinku! Amma, ni duk wannan bai dame ni ba. Abin da ya fi wahalshe ni, doguwar hira. A qare cin abincin dare, a zauna hira, a yi ta yi, a yi ta yi, har wajen qarfe sha xaya, sa'an nan gobe da qarfe bakwai kuma a ce za a ci gaba da irin wannan dogon yawo. Yini tsaye ke nan, kwana tsaye!

"Ran nan M. Isa ya ba ni dariya. Da ya gaji da yawo, a tashi nan qarfe kaza, a koma can qarfe kaza, duk idommu na ga agogo, ba sava lokaci, sai ya ce, Allah dai ya mai da mu inda za mu yi aikimmu, ba duba agogo!.

"Da na ga dai hiran nan ta yi yawa, sai ran nan na yi magana, na ce, a riqa rage tsawon hira! Sai aka ce, wai ai kullum ni a ke jira. Ashe wai a irin wannan taro, ko Gwamna ke wurin, ni ne babba sai na tashi zai tashi. Ashe duk daxewar da a ke yi laifina ne! Don haka, tun da na sami wannan bayani, da an qare shan kofi, an xan jima, sai im miqe, kowa kuwa sai ya miqe, sai Good night! Good night! Watau sai da safe, sai da safe! An tashi ke nan. Nan na sami hutu. Amma da fari, ai na wahala!"[1]

Na ce, "Haqiqa, an sha aiki! Ni abin da na ke tunawa a rai, shi ne yadda soja za su rufe ka da tambaye-tambaye iri iri. Sarki ya ce, "Ai ba a magana. Da tun a gida na shirya zancen da zan yi musu in na je, shafi huxu, har na aiko muku da kofe. Amma da na isa, ya fa karantu? Ya yi tsawo! Ai sai na xauki qusoshin maganar, na hardace, kamar Fatiya. Da ni zatona, na yi magana da soja a wuri dabam dabam sun yi metan, amma wani bature ya ce, 'maganar da ka yi ta fi sau metan!"

Na ce, "ba shakka akwai soja a Burma". Sarki ya ce, "qwarai! Masu yaqi na yi, masu qara koyo na yi. Na ga waxansu masu cewa su sun qosa a kai su fage. Sun gaji da koyo, su sun iya hakanan!"[2]

Na ce, "Allah ya ba Sarki nasara, maganar yi wa soja wasiqu, mun dai rasa dabarar da za a yi. Suna kukan wannan al'amari ba iyaka" ya ce, "Tun da za ni, da wannan na tafi a raina. Na sani muna rubuta musu takardu da yawa da yawa, amma kullum sai kuka su ke, mun qyale su, abin har da ban kunya. Sai da na je na ga inda wasiqummu ke vacewa. An ce muna rubuta wasiqu kamar 2,000 kowane wata, to, ina laifi? Amma cikinsu rabi kawai ke da adireshi mai kyau. Saura duk ba su sa sunan runduna, unit. Sai kuwa an sa sunan runduna a ke iya gane masu su. Ko su, sai an sha aiki. Wani mutum misali yana kamar Barno, sai a bi shi da

---

1 GTK, Ta 126, 6 ga Disamba 1944.

2 *Ibid*, shafi na 2

takardarsa, a sami inda ya ke da qyar. Wani daga can, sai a ce ai yana kwance asibiti a Ikko, to, yaya?"

Abin Da Ya Fi Ba Sarki Sha'awa

Can baya kun ji abin da ya fi ba Sarki mamaki. To, da na tambaye shi abin da ya fi ba shi sha'awa ga mutanen qasar Hindu, sai ya ce, "Kayan aiki! Talakawan qasar Hindu suna aiki da keke, da 'yan qananan mashin fiye da yadda na yi zato. Kusan kowane abu, talakawan Hindu, waxanda na gani, suna da xam mashin, ko xan keke na yinsa. Ga keken shanu, ga na raquma, ga na jakai, ga na alfadarai, kai, kusan komai yana da kekensa. Hatta ban ruwan lambuna da keken shanu su ke yi.

"Da na zo Masar, na yi tafiya ta mil 25, don in gano aikin ban ruwa da shanu. Ina so in yana yiwuwa, in gwada in gani, ko a koya wa talakawa. Domin rashin aikin yi da rani shi ke sanya wahala ga talakawammu. Im ma ka sami nasara ga wannan dabara, da daminu sai mutum ya yi aikin gona da shanunsa, da kaka ya mai da gonar lambu ya yi aikinta da su. Ka ga an hana talakawa zaman banza ke nan, an kuma hana su sai da shanunsu na noma, da rani.

Haqiqa, da yadda talakawan Hindu su ke da himma, da waxannan kayan aiki, da suna da qasa wadatacciya kamar mu, da arzikinsu ya yi yawa. Amma yanzu, sai ka ga talaka da shanun noma, 'yar gonar ba ta yi xan filin nan ba. Ita kuwa ke nan! In ya sami 'ya 'ya, kan wannan 'yar gonar dai za su taru! Saboda haka fatara ta yi yawa ga yawancin talakawan qasar. A xan abin da na gani, ko da ya ke talakawan Hindu sun fi namu kayan aiki, duk da haka talakawan qasan nan tamu da yawa sun fi na qasar Hindu wadata ainun! Nan ga qasa, babu himma babu kayan aiki. Hindu kuwa, ga kayan aiki ba qasa.

"A wajen binciken wannan al'amari na talakawan Hindu, na jiwo wani abu wanda ya ba ni tsoro, kada ya auku a nan qasar. Ashe wai abin da ya sa talakawa suka rasa gonaki sayarwa suke yi ga tajirai. Kana da gonarka sai tajiri ya zo ya zuba maka awalaja mai yawa qwarai, wai zai saya. Talaka da ganin haka, sai ya sayar, ba zai dubi abin da za auku ga 'ya'yansa ba balle, jikoki. Ta haka duk waxansu gonaki suka koma hannun tajirai.

"Ka ga im mu ma ba mu yi hankali ba, irin wannan za ta auku a nan qasar. Ba shakka wannan magana ta qasa, babbar magana ce Tana bukatar shawarwari, da tunani, da duban nesa qwarai qwarai da gaske!" Wannan magana tun a gidan Razdan Sarki ya fara ta har Sarkin Kano ya ce, "Ai ga ta nan ta fara aukuwa a kewayen Birnin Kano!"

Da dai na ga lokaci ya yi nisa, sai na yi ban kwana da Sarki, na koma ma sauki. Da gari ya waye, Ciroma ya xauke ni, muka je har Bici rakiya. Da aka dawo, ni kuma ran nan na yi shiri, Ciroma ya kai ni na sallami Sarkin Kano, sai Zariya Alhamdu Lillahi![1]

A lokacin da Gwamna zai naxa Sarkin Katsina sarauta sai da ya buqace shi da ya taimaka a kai ga nasara a yaqin da ake yi. Abin kamar ya faxi da bakin Mala'iku. Sarkin ya je fagen yaqi ya kuma taimaka gaya wajen karya lagon Jamusawa. Jim kaxan sai ga Jamusawa sun xaga farar tuta, sun bi.

Qarshen Yaqi

Jarumi Xanshuwa ya ce abubuwa uku sun faranta masa rai sosai:

"Na farko dai wanda shi ne babbansu qarewa yaqi. Na biyu kuma kowa daga cikinmu jakarsa a cike take da kuxi, Na uku kuma shi ne saboda mutanenmu suna zuwa. Muna nan muna alla-alla ranar ta zo. Ran nan kawai sai aka ce damu mu tafi tarbensu. Muna nan muna jiran zuwan su can sai ga su sun iso. Allahu Akbar! Yo! dubawan nan da zan yi haka wai ko zan ga idon sani, sai kuwa muka yi ido huxu da marigayi Alhaji Abdulqadir Keftin Makama, Edita na wannan jarida a da, Allah Ya jiqansa.[2]

"Suka ce su masun zo ne musamman saboda su taya mu murna da farin ciki saboda nasara da muka yi a fagen fama, wanda duniya duka ta yaba da irin qoqari da dauriyar zuciya da muka nuna. Ya ce "Mutanen Nijeriya suna gaishe ku."[3]

Ziyar da wannan qungiyar 'yan Jaridu wadda ta haxa da Alhaji Abdilqadir ta qara wa sojojinmu qarfin gwiwa, da alfahari da himmatu. Daga nan sai Bataliyar su Danshuwa suka bar wannan gari suka ta fi wani gari da ake kira Kebin Naga. A lokacin da suka isa wannan gari sai, Babban Baturensu ya tara sojojin gaba xaya ya ce da su:

"To, jama'a yanzu ga shi Allah Ya kawo mu wannan gari saboda haka tun da yaqi ya qare za mu daxe a nan saboda haka idan akwai mai buqatar yin aure yana iya yi a nan, maimakon ku riqa zuwa neman matan banza, da haka wani ya je ya xebo ciwo, wannan kuwa abin kunya ne, amma ba irin aurenku na Baqar Fata ba. Kada ku auri fiye da mace guda."

---

1 GTK ta 126, 6 ga Disamba 1944, shafi na .1-2

2 *Ibid.*, ta 126 1962, shafi na 8

3 *Ibid*.

To, abin nema ya samu! Nan da nan da ya gama yi wa sojoji gargaxi a kan neman karuwai, kuma ga babbar dama an ba su cewa duk wanda yake so ya yi aure. Ai shi ke nan! A kuma wannan lokaci sai aka baiwa sojoji lifi, kowa ya je ya yi nasa shagali. Daga nan sai jarumi Danshuwa ya shiga qulle-qullen, yadda zai bullowa wannan sabon al'amari, saboda ya yi la'akari da waxannan mata ba kininsu ba ne. Inda gizo yake saqar fa ke nan.

Da jarumin ya nitsa, sai ya kintsa 'yan komatsansa ya shiga jirgi bai zame ko'ina ba sai a wani garin Indiya wanda ake kira Madaras. A wannan gari, sai ya sauka wajen wani abokinsa. Bai daxe da zuwa ba, sai yaga waxansu 'yam mata kyawawa guda uku. Ya ce, "Lahaula Wala Quwata! Kai ka ce matan nan Aljanu ne ko kuma su suka yi kansu don kyau. Ai nan da nan gogan naka sai na ruxe, kuma an sosa mini inda yake mini qaiqayi, domin ni da ma babban burin da ya kai ni garin ke nan, kuma da ina so in tuntuvi shi abokin nawa da maganar matan garin amma ina jin kunya. Ashe a wannan garin ne zai yi aure cikin kwana xaya rak.

Kyawawan 'yam mata sun rikita jaruminmu, sai ya ji duk faxin duniyan nan babu abin da yake so illa xaya daga cikin waxannan 'yam mata, ba kuma wadda yake so in ba ita ba. Ya kamu da ciwon soyayyanan take. Amma kuma tana qasa tana dabo don ya rasa yadda zai yi masu magana. Ya ce: "Ashe koko ne yake ba kunun zaqi tsoro, ni ina ganin kamar ba za su yarda da mu ba, ashe su kuma suna ganin kamar mu ne ba za mu yarda da su ba. "[1]

Jarumi dai ya yi ta maza, ya tambayi sunan xaya daga cikinsu, sai to ce sunanta Suwulu. Bai yi wata wata ba, sai ya kawo maganar aure. Da dai ya ji ta yarda sai ya tambayeta irin abin da zai bayar na dukiyar aure, sai ta ce ya ba da rupee saba'in da kuma wani irin goro. An gama! Nan da nan ya tafi ya kawo kuxin da goron. Abin maganar aure dai ta taso wuta – wuta, daga nan sai suka xunguma zuwa wajen iyayenta. Magana fa ta wuce ta wasa. Da zuwa wajen uban wannan budurwa, sai suka shaida masa abin da ke tafe da su. Shi kuma sai ya kira mahaifiyarta ya faxa mata cewa ga Suwulu ta sami miji. Ita ma ta amince. Shi ke nan duk iyayen sun yarda sai maganar aure ta zauna dimirmir. Matar mutum kabarinsa.

To, Allah xaya gari bamban! A wannan lokaci sai aka kira qaninta, aka kuma kira wani Malami mai xaura aure. Abin kamar mafarki, Xanshuwa ya ce:

Ni ina zaton irin aurenmu ne da za a bi waxansu sa ranar aure da sa ranar tarewa. Sai kawai aka kira Malami ya xaura aure, duk gamawa mu da mutum bakwai aka xaura wannan aure: ita da iyayenta, da qaninta, ni kuma tare da abokina, sai kuma Malami mai xaura aure

[1] GTK 17.8. 1962, shafi na 8

Da zuwan Malami sai aka bayyana masa komai, da komai, sai aka ce da ni in kawo hannuna, ita kuma ya ce ta kawo nata, sai ya haxa nawa da nata, sa'an nan ya yi wani karatu cikin harshen Indiya, ni dai ban san abin da yake faxa ba. Da ya yi ya gama, sai ya ce shi ke nan an xaura mana aure, daga lokacin ta zama matata. Sai na ga abin kamar a mafarki, na ga irin yadda a ke shan wahala a qasarmu kafin mutum ya yi aure. Abin mamaki wai an nemi aure cikin kwana guda har an gama komai da komai.

A lokacin ina zaton za a ce in bayar da kuxin gaisuwar Uwa da Uba, da kuxin sa rana da kuxin tarewa, da kuxin kitso, da kuxin sayen baki, da kuxin buxar kai, da sauransu. Sai, kawai aka ce mu tashi mu tafi tare da matarmu, bayan an lilliqa mana furanni. Shi ke nan sai muka shiga mota, ba muyi burki ba sai a barikinmu, na ta fi na nuna wa Baturemmu ita. Da ganinta sai ya tare mu da dariya, suka gaisa, sa'an ya tambayeni inda na auro ta.[1]

Malam Tanimu Zariya Malamin Sojoji

Malam Tanimu Zariya tun yana xan shekara 14 yake zuwa Kaduna daga birnin Zazzau bayan da, Dungurawa suka kammala tarewa a Kaduna. Zirga-zirga ta hanyar jirgi tsakanin Kaduna zuwa Zariya ba wuya. Saboda haka ya kan yi ta karakaina a tsakanin Zariya da Kaduna. Saboda haka kafin ka ce kwabo har ya san Dungurawa a layukansu. Saboda daga Kusfa ya fito, gidan manyan Malaman Zazzau da suka shahara, ya sa Malam Tanimu Zariya cuxanya da shugabanni da attajiran wannan gari saboda haka kusan komai aka yi a Kaduna, shi ganau ne. duk kuma abubuwan da suka faru a Dungurun shi jiyau ne daga waxanda suka gani ko aka yi da su.

Haka kuma yana tare da Sarakunan Zazzau. Wannan ya sa a varkewar yaqin duniya na biyu, a shekarar 1939, sai Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru ya ba da shi, ya zama malamin sojoji, saboda zurfin iliminsa da hankali da kaifin basirar sa. Ya kuma yi suna a ilimin hisabi. Wannan malami ya taimaka wajen koyar da sojoji Addini da kuma sauran harkokin rayuwa kamar yadda ya kamata bisa tsarin musulunci. Saboda haka, da shi sojoji suka dawo Kaduna bayan qarewa yaqi. Wannan ya sa ya san Kaduna, sojojinta da jama'arta, sosai da sosai. Domin haka ne kusan duk bayanansa akan Kaduna ko dai yaji a bakin da baya qarya ko kuma ya gani da idonsa. Ko da yake ba Badungure bane, amma yana xaya daga cikin jama'ar farko da suke tare da su, a lokacin da suka tare. A lokacin da layuka ba su wuce guda biyar ba.

Wannan babban malami ya daxe yana hulxa da tsofaffin soja a jama'ar wannan gari waxanda suka amfana da iliminsa da gogewarsa a wajen tafiyarsa harkokin jama'ar garin Kaduna.

---

[1] GTK 28 Yuli 1961, shafi na 4

A cikin watan Maris na shekarar 1956 ne Jam'iyyar Tsofaffin Soja Reshen Kaduna ta yi taronta don ta sake zaven shugabanninta. Jibrin Farlomi, shi ne aka zava Shugaba. Mataimakinsa M. Isa Nupe, Sakatare M. Idi Sakkwato. Mataimakin Sakatare, M. Sale Dikwa. Ma'aji M. Ramalan Yelwa. Mataimakin Ma'aji, M. Shuaibu Sambo Biu. Sakataren Kuxi, M. Musa Wadai. Oganazin Sakatare M. Idrisu Lakwaja.[1]

Sojojin da suka yi yaqin duniya na farko sun fito da Arewa da Nijeriya baki xaya ga idanun duniya. Qasashen duniya sun farga sun kuma waye da cewa ba albarkar qasa Nijeriya kawai ke da shi ba, a'a har ma da na jama'a kuma jarumai. Abin da sojojin farko suka yi wa Arewacin wannan qasa, har yanzu mutanen wannan sashe suna cin moriyarsa. Da ba mu da jarumai ai da ba mu samu bataliyoyi da makarantun sojoji ba. Da yaqin duniya na biyiu ya varke, sai aka dawo gidan jiya, aka kuma shiga kwasar sojoji. Sojojin yaqin duniya na biyu sun qara nuna wa duniya bajintarsu. Saboda wannan abin da sojojinmu suka yi sai ya qara mana mutunci a idanun Turawa. Idan ka duba ko a yanzu akwai manya-manyan makarantu da bataliyoyin sojoji a Arewacin wannan qasa.

Wannan yaqi ya haifar da matsaloli masu yawa ga duniya, waxannan matsaloli sun shafi Arewa matuqar gaskiya saboda ta ba da gudunmawar dukiya, da kayayyaki da sojoji a lokaci mayuwacin gaske. Alhaji Shehu Shagari, GCFR tsohon Shugaban Qasar Nijeriya ganau ne ga ire-iren waxannan wahalhalu ba jiyau ba. Mai girma Shehu Shagari ya ce, ba zai tava mantawa ba da yadda yaqin duniya na Biyu (yaqin Hitter) ya haifar da matsaloli ga jama'a, da kuma yadda waxannan matsaloli suka shafi xalibai a makarantu. Ya ci gaba da cewa:

"Wata matsalar kuma da xalibai suka fuskanta a wannan lokaci ita ce, ta qarancin abubuwan da suke samun tallafinsu daga wurin Gwamnati domin kuwa al'amarin sai da ya kai munzalin da gwado ake xinka wa xalibai tufafin makaranta. Hatta ma kwanukan cin abinci a xakunan cin abincin xalibai sun yi qaranci, abin da mutum zai iya gani kawai shi ne, akushi da qwarya waxanda xalibai ke amfani da su a wannan lokaci. Sa'an nan kuma a wannan lokaci ne aka vullo wa xalibai da shirin "dogaro-da-kai", aka qirqiro gonar makaranta, a inda kowane xalibi shi ke noma abin da zai ci, kamar dankali ko rogo. A wannan lokaci miya ce kaxai hukumar makaranta ke wadata xalibai da ita, sa'an nan kuma akwai qarancin gishiri, don haka ba a sa wa xalibai gishiri a cikin miya, sai dai kowane xalibi ya kawo gwangwanin sigari a zuba masa, wanda zai ririta har tsawon wata guda.

[1] GTK10 ga Afrilu, 1956, shafi na 11

"A tsakanin wannan lokaci ne kuma aka riqa yawaita cin garin rogo, a inda a kan ba xalibai garin rogo kusan sau uku a rana guda. A dalilin haka ne xalibai suka gundura har suka fara qyamar garin rogo.[1]

"Varkewar wannan yaqi ya kawo koma baya a fagen harkokin ci gaban duniya. Al'amuran ciniki da kasuwanci suka lalace suka tsaya cik. Saboda manyan qasashe masu albarkatun masana'antu na duniya waxanda suka sauya alqiblarsu da sarrafa albarkatunsu ga wannan yaqi. Duk qasashe manya da qanana sun shiga cikin matsi da wahala iri-iri.

"Varkewar wannan yaqi ya jefa duniya cikin mummunan matsi. A Nijeriya an shiga rashin kuxin da za a riqa tafiyar da ayyukan yau da kullum. A dalilin haka ne Cif Kwamishina a Kaduna ya rubuta wa Sarkinn Musulmi Alhaji Abubakar Sadiq takarda a watan Oktoban 1939 yana buqatar da ya baiwa Gwamnati wani kaso daga albashinsa don taimakon yaqi. Gwamnati na buqatar Sarakuna su bada kashi biyar cikin xari na albashinsu. Saboda haka sai Sarkin Musulmi ya aika wa Sarakuna da shugabanni talatin da shida dake qarqashinsa da su taimaka kamar yadda ake buqata."[2] Qasar Ingila da qasashen dake qarqashin mulkinta sun sha baqar wahala. Don haka ne Ingila ta bada Taimakon Bayan Yaqi ga waxannan qasashe.

Ingila ta ba da Taimakon Kuxi

A qarshen wannan yaqin nan Majalisar Ingila ta yarda ta ba qasashen Mulkin Ingila kuxi su gina su asibiti, da hanyoyi, da famfo, da makamantansu. Wannan tallafin kuxi da Ingila ta bayar ya taimakawa waxannan qasashe farfaxowa daga matsalolin wannan yaqi. Qasar Ingila ta kyauta da nuna wannan karimci da tayi, ai wanda ya taya ka xibar zuma, shi ya kamata ya tayaka shanta.

Qarewar wannan yaqi shi ma ya kawo bunqasar garin Kaduna, sojojin da aka kwasa daga sassa daban-daban bayan da aka sallame su sai suka komo da zama a wannan gari. Bayan da yaqin ya qare sai Kaduna ta cika maqil da tsofaffin sojoji. Ba ma qarin jama'ar garin ya samu ba kawai, har ma da na gine-gine da makarantu. A cikin shekarar 1944 aka gina babban asibitin soja da ke Badiko don kula da sojojin da suka tagayyara wajen yaqi. An qare yaqin duniya na Biyu a cikin shekarar 1945.

Saboda matsayin Kaduna na hedkwatar Arewacin Nijeriya da kuma matsayinta wajen horar da sojoji, sai garin ya samu babban barikin sojoji. A wannan gari ne aka samu Sashen Rundunar Soja 'Birged' ta farko, wadda ke

---

[1] Sagir Muhammad da Aliyu Isma'il, *Tarihin Shehu Shagari*, M&I Essence Publishers Kaduna (2003), shafi na 25-26.

[2] Jean Boyd with Hamzat M. Maishanu, Sultan Saddiq Abubakar III: Sarkin Musulmi. Spectrum Biiks Ltd, Ibadan (1991), shafi na 16.

tafiyar da shugabancin sojojin Arewacin lardunan Arewa, ita ce kuma babbar tashar da ke da kayayyakin yaqi na Nijeriya baki xaya a wannan lokaci. A ita wannan qungiyar masu gadi ta soja, 'Garrison' xin akwai bataliya ta uku (3rd Battalion), 1 "Field Battery " da 'yan Atilari (Sojan Igwa masu farmaki daga nesa). Sannan kuma ga Injiniyoyin sojojin Nijeriya duk a wannan Birged da ke garin Kaduna.

Barikin Sojoji

Bayan qarshen yaqin duniya na Biyu, sai Kaduna Cibiyar Arewa ta riqa samun qaruwar Barikin Sojoji cikin hanzari. Don haka sai garin ya zama na sojoji. A shekarar 1913 aka fara kafa rundunar sojoji a Barnawa. Daga wannan lokaci ne sai aka riqa kafa barikokin sojoji a wurare daban-daban Arewaci da Kudancin Kaduna. A qarshen yaqin duniya na biyu, an samo qarin barikoki da ofisoshin sojoji masu yawa a wannan gari. Akwai:

1 York Barracks: wanda yake a shiyar Gidan shawara wato *Lugard Hall*.
2 Ethiopia Barracks: yana tsakanin titin Banki da titin Sakkwato.
3 Hedkwatar Burged ta xaya (1st Brigade): yana tsakanin titin Ahmadu Bello way da titinan Banki da Sakkwato, a shiyar "Kingsway Stores. "
4 Balfour Barracks: wanda aka fi sani da asibitin sojoji.
5 Somme Barracks: na Kakuri.
6 Dalet Barracks: yana kusa da Kawo.
7 Mogadishu Barracks: yana kusa da babbar kasuwa.
8 Brompton Barracks
9 Clayton Barracks[1]

Waxannan Barikoki biyu na qarshe, su ne barikokin farko kafin varkewar yaqi a garin Kaduna. Kaduna gari ne na hedkwatar Birged na farko, ta qasa baki xaya daga shekarar 1914 zuwa 1945. Bayan shekara goma da qare yaqin Hitler, sai a shekarar 1957 aka fara bunqasa Kaduna da Makarantar Horar da Hafsoshin soja, wato *Royal Nigeria Defence Academy* (NDA).

Kafin shekarar 1965, garin har ya samu qarin barikokin soja guda goma sha-uku, waxanda suka haxa da:

1 Bataliya Sojan Ragamar Nijeriya ta Uku wato The Third Battalion Nigerian Army
2 Bataliya ta shida, wato ta Sixth Battalion
3 Nigerian Air Force Base
4 Reconnaissiance Squadron and Regimental Hedquarters

[1] NAK, Zar prof 7/1 251- Military Barracks N.C 26/3/60

5 1 Feild Battary (Artillery)
6 1 Feild Squadron (Engineers)
7 88 Transport Regiment
8 2nd Reconnaissan Squadron
9 2nd field Battery (Artillery)
10 Ammunition Factory (DIC-Defence Industrial Corporation)
11 Nigerian Military Trainnig College (NMTC)
12 44 Military Hospital
13 Ordinance Depot[1]

[1] Madiebo Alexander A, *The Nigerian Revolution and Biafran War, Enugu*, Fourth Dimention Pub, 1980, shafi na 10

KASHI NA BAKWAI

Sarautar Sabon Garin Doka

Sir Bryan, a zamansa na Di'o da yayi a Zariya, ya fahimci Lardin Zazzau sosai. Domin ya iske rikice-rikicen Zariya ya sha bamban da rikice-rikicen ko'ina da ya zauna, musamman Lardin Sakkwato inda ya taso. Saboda haka ne ma ya ce: "Lardin Zazzau, Lardi ne na rundunoni biyu, kowace, runduna ba a bin da ya gamata da 'yar'uwa, harshe dabam, al'ada daban, addini daban. Dukkansu kuma a qarqashin Sarki guda, shi ne Sarkin Zazzau. Yankin Arewa na lardin duk Musulmi ne, na Kudu kuwa garwaye ne na qabilu iri-iri, kowace da harshensu da al'adarsu.

"In Sarkin Zazzau zai aika da hakimi can Kudu, sai ya zavi gogagge a cikinsu wanda ya iya mulki yake aikawa da shi. Misali, akwai wani hakimi a Zangon Katab wanda a ke kira Ja'afaru, xan uwan Sarkin ne Ibrahim. Shi Ja'afaru ya sami kan qasar Zangon Katab sosai, saboda irin kyawawan halayensa. Ba ya son abin da ya tava qabilun qasar. Ta haka qabilun suka riqe shi kamar uba. "[1]

Haqiqa, lardin Zazzau kamar lardin Bauci ya bambanta da sauran larduna. Saboda haka sai mulkinsa yake da wahala sosai. Amma Allah Ya yi wa Sarakunan Zazzau ilimi, da gogewa wajen mulki da kuma hangen nesa. A wannan lardi mai qabilu iri-iri, Sarakunan ba sa qyamar wata qabila komai rashin qarfinta, ba sa kuma daurewa fitsarar wata qabila komai qarfinta. Saboda haka ne kowace qabila da ke kowane gari a wannan lardi, sai da aka tabbatar tana qarqashin hukuma; tana kuma kai harajinta a lokacin da aka buqaceta. Akwai kyakkyyawan tsarin mulki wanda ya samo tushe tun daga mulkin Fulani. Wannan tsarin ne Turawa suka tarar a lokacin da suka shigo wannan makeken lardi.

A wannan lardi ne kuma aka kafa garin Kaduna wadda ta zama cibiyar tafiyar da mulkin Turawa a Arewa. Koda Gwamna Lugga ya ga akwai tsarin mulkin Fulani mai kyau a Arewa, abinka da masanin mulki, sai da yaba ma Sarakunansa. Don haka ne da ya angije Daular Usumaniyya a shekarar 1903, bai vata wani lokaci ba sai ya tafiyar da mulkinsa takan Sarakunan Arewa, wani samfurin mulki da ya kira *Indirect Rule*. Garin Kaduna kuma ya zama tushen tafiyar da wannan mulki, qarqashin ikon Gwamna. Amma tun daga kafa wannan gari, sai Sarakunan Zazzau suka shiga qoqarin mallakar wannan gari ta mulkin Sarautar Zazzau.

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 19

Iyan Zazzau Malam Abdullahi, shi ne wanda Sarkin Zazzau Alu ya turo ya riqe muqamin Hakimi a Kaduna. Shi Iya Abdullahi, xa ne ga Tajo wanda shi kuma qani ne ga Sarkin Zazzau Alu Xansidi. Saboda himmarsa da gogewarsa a harkar shugabanci sai aka turo shi ya riqe mukamin gargajiya a wannan sabuwar hedkwata. A wannan lokaci yana zaune ne a garin Kinkinau daga baya aka koma da shi Afaka.[1]

Iya Abdullahi shi ne wakilin Sarkin Zazzau wanda ya yi aiki da Turawan Mulki, ya kuma taimaka gaya wajen habaka garin Kaduna. Ya yi ritaya a shekarar 1931. Kaurukan Kaduna na karqashin mulkin Zazzau, amma banda sabon garin Doka.

Sabon garin Kaduna bai komo qarqashin mulkin Zariya ba sai a cikin shekarar 1934, a lokacin Sarkin Zazzau Malam Ibrahim. A wannan lokaci ne Sarkin ya bayyana buqatar naxa Sarkin Sabon Garin Doka.

Vullowar wannan maganar sarauta, sai jama'a 'yan takara suka tashi neman wannan sarauta. Har 'yan Saliyon nan, Mista Thompson, da Mista Johnson, da Mista Nortey da kuma Malam Aminu Bayaraben Ilori, sai suka tashi neman sarautar haiqan. Su 'yan Saliyon a wannan lokaci suna da kuxi tare da xaurin gindin Turawa, sai suka ga ba abin da ya rage sai yin sarauta kawai. Domin ganin wannan abu, sai Sarkin Zazzau Ibrahim ya ce da 'yan Saliyon nan (Ko da yake sun riga sun zama 'yan qasa) Ku ba musulmai ba, sarautar Musulmi zai yi wuya a wajenku, Ko da yake yanzu Kaduna qaramin gari ne ba wanda ya damu da shi, amma fa nan gaba za ta bunqasa ta gagari wanda ba Musulmi sarautar ta ba, shin masu neman wannan sarautar musulunta za su yi?[2]

Jin wannan kalamin Sarkin Zazzau dai sai suka janye daga takarar neman sarautar Sabon Garin Doka, amma Mista Thompson sai ya ce atafau sai ya yi sarautar. Wajen maganar musulunci kuwa ya musulunta ya maida sunansa Malam Isa ya fito ya duqufa wajen cin sarautar. Takarar neman sarautar garin sai ta tsaya tsakanin Malam Isa Thompson da Malam Aminu Ilori.

Malam Aminu Ilori dai attajiri ne babba, xan kwangilar Fidaburdi. Shi mutum ne karimi mai son addini kuma ma'abucin kyauta. Ya yi aikin 'rate collector,' (Mai karvar harajin fuloti etc.), yana kuma xaya daga cikin Shugabannin bariki, wato 'yan majalisar gari. Shi mutum ne wanda a kullum qofar gidansa ba ya yankewa da jama'a, idan kuma ya yi hawan doki sai ka gan shi tamkar wani Sarki. Saboda kwarjininsa, tun wajen shekarar 1920 ake zarginsa da yana xaukar kansa tamkar

---

[1] Abdulqadir Y. Sambo, *Tarihin Garin Kaduna*, shafi na 3

[2] M. Tanimu Zariya a Kaduna a ran 4 ga Agusta 1984.

Sarki. Shi wannan attajiri, Allah Ya yi masa kwarjini, domin haka ne abokan hamayyarsa ke raxe-raxin yana taqama kamar Sarkin Kaduna.[1]

Saboda murtukewar neman wannan sarauta tsakaninsu, sai Sarkin Zazzau Ibrahim ya bar riqon gari a hannun Malam Aminu kafin a zavi wanda za a naxa shi sarautar garin. Daga baya sai aka naxa Muhammadu Sarkin Daji sarautar Sabon Garin Kaduna. Hakimcin garin kuma ya koma hannun Wambai Usman, Hakimin Igabi. A wannan lokaci kuma magajin gari, Muhammadu Sambo yana sarautar Sabon Garin Zariya.[2]

A matsayin Kaduna na sabuwar hedkwatar Arewa, sai ta zama ita ce tushen mulki. Domin kuwa a nan ne fadar Gwamna take da shi da 'yan majalisar mulkinsa, waxanda suka qunshi: Kwamishinan 'yan Sanda, da Kwamandan Soji, da Daraktan Fidaburdi, da Babban Likita mai kula da Lafiya, da sauran muqarrabansa. Daga wannan hedkwatarce, ake zartar da hukunci da doka, a kuma aika su ga Razdan wanda kuma zai aiwatar da doka ko hukunci takan Sarakuna zuwa ga jama'arsa.

Amma tun kafin zuwan Turawa, akwai hanyoyin mulki wanda ake bi domin zartar da doka ko hukunci, a wannan yanki na Kaduna. Alal misali, akwai Magaji Jisambo a garin Maqera da Iyan Gari a Kangiwa wato Kinkinau, da Turaki Babba a garin Rigachikun. Ta waxannan masarautu ne Sarkin Zazzau ke isar da iko akan jama'arsa. Saboda kowane gari yana da garuruwa da qauyuka a qarqashinsa.

Da aka kafa sabuwar hedkwata sai mulkin Zazzau ya zama bai shafi Kaduna ba saboda kada a riqa taqon-saqa tsakanin masarautar Zazzau da mulkin Gwamna. Amma duk sauran, garuruwa da qauyuka da ke kewaye da Kaduna suna qarqashin mulkin Sarki ne kamar gururuwan da ke gavar kogin Kaduna.

Daga shekarar 1913 ne saboda kwararowar leburori zuwa Kaduna sai ga xaruruwan leburori sun haxu amma ba su da iznin zama a Sabon Garin Doka, domin su ba Dungurawa ba ne. Wannan ya tilasta a yi masu tsangaya ta musamman a wajen kasuwar Panteka Tsohuwa da ke kusa da Makarantar Kimiya da Fasaha wato "Kaduna Polytechnic " a yanzu. Ana kiran wannan tsangaya "Labourers' Camp, " wato Tsangayar Leburori. Amma kafin ka ce kwabo har wannan tsangaya ta cika maqil da jama'a, waxanda ba sa qarqashin hukumar Gwamna ko ta Sarki. Ko da yake an naxa Mista M.C. Green da ya kula da tsangayar, aikinsa bana mulki ba nena ganin aikin gine-gine na tafiya sosai ne aikinsa.

Saboda haka sai aka maida wannan Tsangayar Leburori wadda daga bisani a ke kira Unguwar Leburori, a qarqashin Iyan Gari da ke Kinkinau. Domin ya sa waxannan jama'a qarqashin hukuma, sai Iyan wannan lokaci Abdullahi ya yi mata

---

[1] M. Tanimu Zariya a Kaduna a ran 4 ga Agusta 1984

[2] Hira da Ibrahim Sarkin Unguwar Shanu ran 8 ga Agusta 1984.

Sarki ya kuma so ya sauya mata suna da Unguwar Yalwa. Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim Xan Sarkin Kawo Abdullahi yana da shekaru goma sha-shida a lokacin da wannan al'amari ke faruwa a gabansu. Ga abin da ya ce: "Asalin wannan Unguwar Lebura a wajen Panteka ta yanzu aka kafata. Da ta zama qarqashin Iya Abdullahi sai ya yi mata Sarkin Yalwa wanda aka yi wa wannan sarauta kuwa shi ne Kwasau. Kwasau a lokacin da ya sami sarauta yana riqe da muqamin Jakadan Sarkin Kawo Abdullahi. Amma duk da wannan naxi, jama'a sai suka ci gaba da kiran wurin Unguwar Lebura ba Unguwar Yalwa ba. "[1]

A shekarar 1922 an sami canje-canje a tsarin mulkin wannan yanki da ke qarqashin, mulkin Zazzau a lokacin Gwamna H. Clifford. A wannan lokaci ne a kafa Tudun-Wada.

Wani abin tambaya a nan shi ne in Tsangayar Lebura na qarqashin mulkin Zazzau, to, me zai hana a haxa da Sabon Garin Doka? Abin da Sarakunan Zazzau suka so su samu ke nan tunda farko. Turawan mulki kuma sun qaiyade mazauna Sabon Garin Doka. A shekarar 1915 aka naxa Mista Macregor, a matsayin sabon Jami'i mai kula da shari'a da Sha'anin Mulki, a cikin Sabon Garin Doka. Wannan ya qara maida Sabon Garin a matsayin Gari, wato "Kaduna Township. " Amma duk da haka an qi a ci gaba da maida garin qarqashin mulkin Zazzau. Saboda Turawa na gudun ka da a samu rikice-rikicewajen mulkin Kaduna Township da masarautar Zazzau. Ita Masarautar Zazzau kuma na gudun ka da Turawa su yi mata Sarki. Domin kuwa duk da yake wajen bai wuce layuka biyar ba saboda sun hangi garin zai bunqasa sosai a zuwa gaba. Sarkin Ibrahim Unguwar Shanu ya ba da wannan bayani inda ya ce: "A wani bikin Sallah da aka yi a Sabon Garin Doka, wanda Sarkin Zazzau Alu Xan Sidi ya halarta, sai M. Aminu Ilori ya yi shigar sarauta. Saboda haka sai Sarkin Zazzau ya yi qararsa ga Razdan a Zariya. Sarkin Zazzau Alu, ya yi qoqarin karvar Kaduna ta koma qarqashinsa, amma bai yi nasara ba. Shi ma Sarkin Zazzau Dalhatu ya yi na sa qoqari, amma abin ya faskara. Sarkin Zazzau Ibrahim ne ya cimma nasarar mallakar Kaduna. "[2]

An ce Sarki goma zamani goma. Da Sarkin Zazzau Ibrahim ya qarvi mulkin Kaduna a shekarar 1934 sai ya kawo nasa sauye-sauyen. A wannan sabon zubi sai aka sauke Iya Abdullahi. Aka maida Kaduna qarqashin Wambai Usman da ke Hakimci a Igabi. Aka kuma naxa Sarkin Daji Sarkin Sabon Garin Doka. A wancan lokaci an nemi a turo 'ya'yan Sarakunan Zazzau da su zo su riqe Sarautar Sabon Garin Doka, amma sai ba su nuna sha'awar zuwa wannan gari ba, saboda 'yan layukansa qaxanne, ga kuma jama'ar garin da halin barikanci, wani hali da

---

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim a gidansa a ranar 15 ga Satumba na shekarar 1984.

[2] *Ibid*.

yake sabo a Arewa. Bayan rasuwar Sarkin Zazzau Malam Ibrahim Xan Kwasau a shekarar 1937, sai Malam Ja'afaru Xan Isyaku ya zama Sarkin Zazzau.

Sarkin Zazzau Ja'afaru, sai ya kawo nasa canje-canjen. Ya xauko Malam Muhammadu Aminu Sambo, yana sarautar Sabon Garin Zariya, ya naxa shi Sarkin Sabon Garin Doka a shekarar 1938. A shekarar 1945 aka qara masa girma ya zama Magajin Gari. Saboda haka mulkinsa sai ya haxa da sauran Unguwanni waxanda suka haxa da Tudun-Wada, da Afaka, da Sabon Birni, da Maqera, da Barnawa, da Unguwar Shanu, da Unguwar Sunusi, da Abakpa, da Kakuri-Gwari, da Tudun-Nufawa, da sauran wurare duk sai su ka koma qarqashinsa. Sarkin Zazzau Ja'afaru gwanin mulki ne, ya yi amfani da gogewa wajen harkar jama'a, da ilimi da ilhama wajen mulkin Zazzau. kuma zaven Malam Muhammadu Sambo da wannan muqami ya dace sosai. A matsayinsa na xan Sarkin Zazzau, sai ya riqe Magajin Garin ya yi muhimman ayyuka da su ka bunqasa Kaduna, da sauran garuruwa da ke kewaye da shi.

Da Malam Aminu sambo ya sami wannan muqami, sai aka naxa Rejimanci Malam Baqo Sarkin Sabon Garin Doka, aka kuma yiwa manyan qabilun garin sarauta. Aka naxa Malam Babale Sarkin Hausawa da Balogun Sarkin Yarbawa da Maliki Sarkin Nufawa. Waxannan shugabanni da Sarakuna sun taimaka gaya wajen kawo zaman lumana da ci gaban wannan gari.

A shekarar 1956 sai aka kawo wani sabon shiri, inda aka raba Kaduna da Zariya. A wannan sabon yanayi sai aka maida Kaduna ta koma Yankin Qasar Hedkwata wato *Kaduna Capital Territory*, a zamanin Mista McCullum wanda yake riqe da muqamin Kantoma kuma Di'o.

A shekarar 1974 sai aka qirqiro Mulkin Qaramar Hukuma a Kaduna wato *Kaduna Local Government*. Wannan ya kawo shirye-shiryen mulkin wannan gari. Sakataren mulki ya maye gurbin Kantoma. An kuma kara qarfafa da bunqasa Sarakuna a cikin wannan sabon tsari. Haka kuma da Sakatarorin Mulki na Qananan Hukuma da Sarakunansu duk suna qarqashin Shugabancin Alhaji Nuhu Bamalli Magajin Garin Zazzau, MP, CFR.

Waxanda suka fara riqe muqamin Sakataren Qaramar Hukumar a Kaduna su ne: Alhaji Balarabe Mahmud, da Alhaji Abdullahi Abubakar, da Alhaji Junaidu Yahya, da Mista Musa Yohanna, da Alhaji Ahmed Dalhatu. Kowanensu ya ba da tashi gudunmawar ga ci gaban Kaduna. A vangaren Sarakuna kuma sai aka naxa Hakimai guda biyar. Wanda ya naxa su shi ne Alhaji Nuhu Bamalli. Haka kuma waxannan Hakimai suna qarqashin Babban Hakimin Kaduna Sarkin Doka, Alhaji Zakari Isa.[1]

[1] Hira da Alhaji Zakari Isa, Sarkin Doka Hakimin Kaduna, 20 ga Satumba 1984.

Kafa Kaduna Yankin Hedkwata

A cikin dokokin da Majalisar Wakilai ta Jihar Arewa za ta duba a wani taro nata da ta buxe, har da maganar fid da Kaduna daga hannun En'e ta Zariya, wato ta yi zaman kanta. Saboda Unguwar Turawa na Kaduna na qarqashin Kantoma ne da Razdan na Zariya. Su kuwa gwamnatin Jiha ce ta wakilta su su duba wannan wuri. Cikin garin Kaduna kuwa da 'yan qauyukan da suka kewaye, alhakkin En'e ta Zariya ne ita ke tafiyar da sha'anin yau da kullum.

Yadda labarin yake a cikin Gazette ta Jihar Arewa, ance saboda qaruwar girman Kaduna wajen yawan mutane da arziqi da kuma muhimmancinta ga zama hedkwatar jiha,an ga wajibi ne a zame ta daga hannun En'e tayi zaman kanta. Tunda da daxewa gwamnatin Arewa ta naxa kwamiti wadda zata bincika waxansu canje-canje da ya kamata a yi wajen mulkin garuruwa masu muqamin birane wato "Urban Areas. " Kwamitin nan ya ba da rahotonsa a shekarar 1955, a ciki har ya ba da shawara cewa zai fi kyau Kaduna kujerar gwamnatin jiha ta koma hannun gwamnati.

In an tuna garin Kaduna sabon kafi ne da bai fi shekara hamsin ba a lokacin da maganar ta taso. gwamnatin Lugga ne ya sa a kafa wurin, a lokacin wurin fili ne kawai ba 'yan qasa zaune a wurin gine-ginen gidajen Turawa da ofisoshin gwamnati su ne a sannu-sannu suka dinga jawo jama'a, har garin ya zama yadda yake a yanzu.

Da zarar an gama waxansu shirye-shirye bayan tabbatar da wannan doka, alhakkin sarrafad da Kaduna zai zama xawainiyar gwamnatin Jihar Arewa a cikin Majalisa ne. Za ta zama Hedkwatar Arewa, ba ruwanta da kowane lardi kowata qungiyar mulkin En'e. Za a naxa wani Baturen mulki a matsayin kantoma wato *Administrator*, da mataimakinsa, madadin Gwamna cikin Majalisa za su ci gaba da duba sha'anin Kaduna.

Haka kuma gwamnati za ta kafa kwamiti mai ba da shawara wato *Advisory Board*, kan al'amuran Kaduna.'yan kwamitin za su sami wani Baturen mulki .Administrator, da mataimakinsa waxanda su ne za su duba Kaduna, da wakili xai-xai daga qananan Majalisu biyar da gwamnati, a Majalisar za su naxa kamar sha'anin ciniki, ilimi da sana'o'i. Akwai kuma waxansu mutane biyu da za a naxa su wakilci fidaburdi, da kiwon lafiya,da waxansu mutane da su 'yan kwamiti za su zavo.

Su waxannan wakilai, aikinsu shi ne ba da shawara kan abubuwan da su ka shafi Kaduna. An ce suna iya ba da shawara ga gwamnati kan ta kawo wa ta doka da za ta taimaki garin. Akwai garuruwa da suke da tsari irin wannan, Kamar Enugu, Hedkwatar Jihar Gabas, ita ma tuni ta zama ba ta da qarqashin kowace En'e, tana zaman kanta ne kamar yadda za a maida Kaduna. Qarewa ma Ikko, Hedkwatar Nijeria, ba ta qarqashin kowa, gwamnatin Nijeriya ke duba ta. Da wannan batun fidda Kaduna ya taso haiqan sai aka tattauna maganar a Majalisa.

Fidda Kaduna Daga Zariya

Kafin a raba Kaduna da Zariya, wato ta kasance ta fita daga qarqashin mulkin Zazzau, dole A lura da waxansu canje-canje da aka yi a shekarar 1938, wanda Malam Ja'afaru ya yi. Waxannan sauye-sauyen sun shafi dukkan gundumomin lardin Zazzau ne, musamman Hakimai. A lokacin ne Magaji Muhammadu Sambo aka naxa shi Sarkin Sabon Gari. Wannan canji shi ne ya yi sanadiyyar da ya sa aka haxa Kawo, Maqera, Barnawa, Afaka da kuma Tudun-Wada suka zama a qarqashin mulkin gundumar Rigachikun. Daga baya aka sake xauke waxannan wurare aka mayar da su qarqashin mulkin gundumar Sabon Garin Kaduna. Bayan da Magajin Garin Zazzau ya rasu, sai aka naxa Muhammadu Sambo ya zama Sabon Magajin Garin Zazzau a shekarar 1945. A shekarar 1940 ne aka qirqiro ofishin Kantoma, wanda zai riqa kula da garin Kaduna; wadda take kafin wannan lokaci, tana qarqashin Di'o ne na Razdan na Lardin Zazzau, kamar yadda aka yi bayani.

An fara maganar vulguce Kaduna daga yankin mulkin Zazzau, a ranar 18 ga watan Fabrairun shekarar 1954. Don an sami takarda ta ranar 11 ga watan Maris xin shekarar 1954, wacce take tamkar matashiyar maganar da Ministan Qananan Hukumomi da taimakon kai da kai ya rubuta wa Razdan na Lardin Zazzau. Ya bayyana masa cewa nan ba da daxewa ba za su yi taron Majalisar Zartarwa dangane da cire Kaduna daga Zariya, domin gwamnati ta gudanar da mulkin garin Kaduna kai tsaye. Bayan Majalisar Zartarwa ta zauna ta gama tattauna wannan magana da Minista, ya faxa za a tattauna, amma sai a ranar 19 ga watan Maris xin shekarar 1954. Razdan na Lardin Zazzau ya sake samun takarda da ke cewa an tattauna maganar, kuma En'e ta Zariya ta amince da maganar, sai dai batun iyaka da suka bayar a yi. Sai wani taro da aka yi tsakanin Leftana – Gwamna da Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru a ranar 25 ga watan Yunin shekarar 1954, a inda suka qara tattauna batun raba Kaduna da Zariya. Malam Ja'afaru ya bayyana cewa ya yarda da shi da mutanensa na gwamnati ta gudanar da mulkin Kaduna kai tsaye, amma da sharaxin kada a naxa kowa a matsayin 'Sarkin Kaduna'. Ban da wannan ya bayar da waxansu muhimman sharuxxa saboda hangen nesansa, wanda ba duka mutum ne a lokacin zai hango muhimmancin hakan ba, sai dai yanzu. Hakan kuma ta kasance.

Game da tattauna yadda za a tsara iyakar Kaduna da Zariya kuwa, akwai Kwamiti na musamman wanda aka naxa domin yin aikin. Malam Ja'afaru ya naxa Sarkin Kakuri da ya wakilce shi dangane da wannan al'amari. Sauran 'yan Kwamitin sun haxa da Magajin Gari da kuma wani mutum da ban sami cikakken sunansa ba a matsayin shugaban Kwamitin. Wannan Kwamiti ya zauna don gudanar da aikinsa a ranar 3 ga watan Agustan shekarar 1954, a inda ya tattauna muhimman abubuwan da Malam Ja'afaru ke buqata dangane da raba Kaduna da Zariya. Dukkan abubuwan da 'yan Kwamitin suka zartar, a qarshen bayaninsu sun

nuna cewa, sai idan Sarki ya gani kuma ya amince, kafin a soma yin aiki da komai.

Lokacin da aka cimma yarjejeniyar muhimman abubuwa da Malam Ja'afaru, sai aka shiga tsare tsaren yadda za a gudanar da mulkin Kaduna ta fuskar kuxi da ma'aikata; wato xaukarsu da canjin waxansu zuwa Zariya da kuma yadda za a biya diyyar waxansu gine-gine da dole ne a sake yin irinsu a Zariya domin gudanar da aiki. An ce a ranar 31 ga watan Maris xin shekarar 1956, da la'asar Malam Ja'afaru ya sanya hannu dangane da yarjejeniyar da aka yi na raba Kaduna da Zariya. A ranar 1 ga watan Afrilun shekarar 1956 Kaduna ta soma cin gashin Kanta.

Majalisar Wakilai ta zartar da batun nan na fidda Kaduna daga mulkin En'e ta Zariya, bayan an yi waxansu 'yan gyare-gyare kaxan. Gyaran da M. Ibrahim Imam Shugaban 'yan Hamayya a Majalisa ya kawo na dakatar da dokar sai bayan wata shida tukun, ba ta karvu ba. Lokocin da aka yi wa dokar karatu na uku, Firimiya, kuma Ministan Mulkin En'e ya kawo waxansu gyare-gyare, Majalisa kuwa duk ta yarda da su. Wakilai da damasun yi jawabi kan dokan nan. An kuma tafka mahawara a Majalisa Alhaji Sa'adu Alanamu, Ilori: Ya miqe ya ce:

"Lokacin da a ke muhawara kan jawabin Gwamna, wani Wakili abokina daga Kano ya ce abin da waxansu mutane za su yi cikin shekara hamsin, yanzu shi ne abin da gwamnatinmu ke yi cikin shekara huxu tun lokacin da ta xauki matsayinta (Aka varke da murna). Wannan doka, an kawo ta cikin lokaci an kuwa yi maraba da ita da yabawa, ba mutanen Kaduna kawai ba duk ma Jihar Arewa.

"Sa'adu ya ce "tun lokacin da aka haife ni. Kaduna ce hedkwatar Arewa, amma yanzu ne akafi kulawa da ita. Idan aka zatar da dokar nan, muna so mu ga an yi canje-canje da dama. Muna so mu ga Kaduna ta cancanci zama babban birnin Arewa. Mun ji kunya qwarai lokacin Ziyarar Sarauniya, da mutane suka zo daga ko'ina daga Arewa, suna tambaya ko wannan ce Kadunar tamu hedkwatar Arewa? Duk titin qura ne – ba su da kyaun gani ma. Muna fata dai za a kula da tsabtar garin. Amma kuma mu yi hankali qwarai kada waxanda ba 'yan Arewa ba, su danne mu a majalisun da za a kakkafa. A yi doka game da fuloti wadda za ta hana gida ga waxanda ba 'yan Arewa ba. In kuwa ba haka ba, jikokinmu ba za su sami wurin zama a Kaduna ba. "[1]

Yana zaunawa sai Mallam Muhammadu Dodo Katsina ya miqe ya yi magana ya nuna goyon bayan mai magana da cewa: "Ba shakka gwamnati ta yi dogon tunani kan wannan magana. Mutane kowane lardi na Jihar nan suna kishin da

[1] GTK 20 ga Maris, 1956, shafi na 6

Kaduna take qarqashin En'e. Duk mutanen Jihar Arewa za su yi farin ciki idan suka ji za a fidda Kaduna daga Mulkin En'e ta Zariya. "[1]

Shi kuwa Malam Hassan Makaman Abuja cewa ya yi: "Kowane lungu mutum yake zaune a Arewa zai yi alfahari da Kaduna. Ina kawo shawarwari da cewa an zatar da dokan nan, a kyautata kasuwar Kaduna ta yanzu, sa'an nan a yi tashar mota. A kyautata qauyukan nan da ke kewaye da Kaduna – Tudun Wata, da Kakuri, da Kawo da sauransu. "[2]

Ra'ayin Malam Bawa Bulkacuwa Bauci ya bambanta da waxanda suka yi magana domin shi cewa ya yi: "Rashin Kaduna ga En'e ta Zariya babban rashi ne kuwa. Saboda haka ina roqon Minista ya ga lallai am biya Zariya ramako. (Wakilai suka ce, a'a, a'a). Dukkan titunan Kaduna a shafa masu kwalta, lantarki da ruwansha su wadace su, a kuma shuka itatuwa masu ba da inuwa. Ina kuma roqon Majalisar Wakilai, don ba zai yiwu ga wani ya shiga zave a Kaduna ba (Alhaji Sa'adu Alanamu: Me zai hana? Nan gaba idan za a sanya wa wani titi suna a Kaduna, a sanya masa sunan Katagum). "[3]

Daga nan ne sai Malam Dauda Qwoi, Zavavven Wakili ya ce: "Majalisun da gwamnati ke son kafawa a Kaduna ya kamata su zama na sosai ne, ba irin majalisun nan da za su kawo ruxarwa ba. Zai fi kyau idan Gwamna-Cikin-Majalisa ya zavi waxannan Majalisu. Shugaban majalisun kuma su kasancewaxanda za su iya aikinsu sosai ne. Na sani En'e ta Zariya ta yi abubuwa da dama a Kaduna. Za mu yi farin ciki idan am biya En'e ta Zariya ramako. To, kuma yanzu me zai faru ga malaman En'e da ke zaune a Kaduna, waxanda suka ji daxin zama, ba su kuwa so su tashi? Ina so gwamnati ta duba irin waxannan mutane. "[4]

Shi kuwa Alhaji Ahman Pategi Ilori sai ya ce: "Na gode wa Firimiya da ya kawo wannan doka xakin nan. Lokacinta ya yi kam. Don ba da daxewa ba Kaduna ta sami sa albarka daga Sarauniya. Wannan taro da aka yi a Kaduna, har abada ba za a manta da shi ba. Wannan doka ya qara sanya Firimiya da Ministocinsa sun shahara kan babban aikin nan nasu lokacin da su ke riqe da muqaman nan. Kaduna tana da manyan dalilai biyu na zamowa hedkwata, ban da zamowa tushen gwamnati, (a) ta fi zamowa tsakiya, (b) za a fi gane ta wajen zamowa tsakiyar hanyoyi, wato hanyoyin mota da na jirgin qasa. Idan dai ana so Kaduna ta zama hekwatar Arewa ina fata gwamnati ba za ta manta da 'yan Arewa, waxanda ke wurin tun lokacin da Lord Lugard ya kafa Kaduna, ba (Malam

---

1 GTK 20 ga Maris, 1956, shafi na 6

2 *Ibid*.

3 *Ibid*.

4 *Ibid*.

Ibrahim Imam: "Nawa ne ke da rai yanzu? " Tana yiwuwa dukansu sun mutu, to, amma 'ya'yansu da jikokinsu suna nan. Kada kuma a manta da Nufawa. A riqa ba su gidaje da 'yanci su yi yadda suka ga dama da gidajensu. Ina kuma son Firimiya ya gaya mini yawan kuxin shiga da na kashewa na garin Kaduna. Ina godewa En'e ta Zariya waxanda suka bari za a xauke garin Kaduna da kewaye, su zamasuna zaman kansu. Ina fata gwamnati za ta ji tausayin En'e ta Zariya. "[1]

Daga nan sai Majalisa ta saurari bayanin Mr. Benjamin Akiga, Binuwai wanda ya ce: "Muna iya tunawa lokacin da ba Kaduna ma, amma hekwatar Arewa a lokacin Zungeru ce, amma shugabannin gwamnati masu wayo a lokacin suka ga zai yi amfani su maido hekwatar nan Kaduna. Kwana biyu ke nan da muka yanke shawara cewa Arewa ta zama xaya dukanta. Ina so in tuna wa gwamnati cewa da yake Kaduna tana cikin mulkin En'e ta Zariya ne, to, kada su manta da Sarkin Zazzau idan ana shawarwari kan iyakar Kaduna da lardin Zariya, don kuwa wannan qasarsa ce ta al'ada. "

Bayan kowane Wakili ya bada shawarwarisa, an sussuke an kuma sheqe matsalolin da ke cikin wannan batu na vulguce Kaduna daga mulkin En'e ta Zariya, an bi komai filla-filla cikin hankali, da natsuwa da lura, sai Sardauna ya miqe ya ba da amsa. Firimiya ya ba Wakilai amsa. Bayan duk wakilai sun gama mahawara kan karatu na biyu na dokar fid da Kaduna daga cikin mulkin En'e ta Zariya, sai Firimiyan Jihar Arewa, kuma Ministan Mulkin En'e ya miqe ya riqa ba su amsa bi da bi. Da farko tukun sai da ya godewa wakilan da suka yi maganar goyon bayan dokar. Ya kuma ce akwai waxansu waxanda basu sami damar magana ba. Akwai wani abu da Larabci ya ce: "Mahaqurci dai ai mawadaci ne. " (M. Ibrahim Imam: Ba dai wajemmu ba).

Firimiya ya ce Wakili daga Ilori ya yi magana game da kyautata aikin tsabta. To, ina tabbatar masa cewa an yi tanadin yin haka tun daga 1 ga Afrilu, na wannan shekarar 1956 Makaman Abuja ya ce a kyautata kasuwar Kaduna. To, tun daga 1 ga Afrilu, za a kashe fam dubu talatin £35,000 don kyautata mayanka da sauran wurare a kasuwar. Game da tashar mota kuwa, muna jira mutane su tashi daga waxansu wurare, sa'an nan a fara aikin.

Malam Dauda Kwoi daga kudancin Zariya ya tambaye ni halin da malaman En'e na Zariya su ke ciki. To, ina tabbatar masa, waxanda aka ga suna da amfani za a san abin da za a yi da su kamar yadda dokar ta ce. (Malam Ibrahim Imam to, waxanda ba su da amfani fa?) sai Sardauna ya ce da shi: kai ma ka san amsar wannan. "A da kai ma ma'aikacin En'e ne – shugaban ma'aikata ma – me ka yi ga ma'aikatanka marasa kyau? " Sai Sakataren Kuxi ya ce: Me kake yi wa kanka? Dajin haka fa sai majalisa ta varke da dariya.

---

[1] GTK 20 ga Maris, 1956, shafi na 6

Game da fuloti kuwa, Firimiya ya tabbatar cewa, "In dai ina kan aikin nan, ba zan yarda a saida qasar Arewa ba. Kaduna ita ce za ta zama babban birnin Jihar Arewa. Ba a yi niyya ba, kuma ba a da niyya wannan birnin Arewa namu ya zama ba mutanen da ke cikinsa ne za su yi mulkinsa, ba wato kamar Ikko ke nan. Malam Ibrahim Imam ya kaxa baki ya ce: "Ko da mun sami mulkin kai? Ai muna mulkin kammu ne ", amsar da Sardauna ya bashi ke nan.

Wane amfani mutanen da ke zaune a Kaduna suka samu daga wannan? Kamar yadda na bayyana wa xakin nan, gwamnati ta yi niyyar kafa Hukumar Ba Da Shawara, wadda za ta riqa yin shawara kan abubuwan da suka shafi mutanen Kaduna wajen kyautata zamansu. An yi tanadin kafa Majalisu ta kan hanyar mulkin En'e. Waxannan majalisu zavavvun mashawarta za su fi yawa cikinsu. Sai Alhaji Sa'adu Alanamu ya ce: 'yan Arewa. "Ina fatan haka,[1] Inji Firimiya. gwamnatin Firimiya ta faxa da cika wa ce. Duk alqawuran da ta xauka sai da ta cika su, sai waxanda ba a yi ba saboda garma ta karye da sauran aiki.

Kaduna Ta Koma Qarqashin Zariya

Kaduna ta samu wajen shekaru talatin da huxu a matsayin Yankin Hedkwata. A cikin waxannan shekarun ta zama hedkwatar Jihar Arewa ta Tsakiya bayan an raba Nijeriya zuwa jihohi goma sha-biyu a shekarar 1967. A wannan lokaci ne aka raba lardin Zazzau zuwa Qananan Hukumomi guda shida da suke da hedkwatocinsu a Ikara, da Zariya, da Igabi da Kachiya, da Jama'a da Kaduna. A dalilin wannan sabon tsarin sai Kaduna ta zama xaya daga cikin Gundumomi goma sha-bakwai da ke qarqashin masarautar Zazzau a zamanin Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu.[2]

A wannan lokaci ne kuma gwamnatin jiha ta naxa shugabannin qananan hukumomi. Alhaji Nuhu Bamalli, Magajin Garin Zazzau sai ya zama shugaban Qaramar Hukumar Kaduna. Shi ne ya havaka sarautar gargajiya a 1974, a lokacin da ya qirqiro gundumomi huxu a garin Kaduna. A shekarar 1976 ne gwamnatin Mulkin soja ta sake sabon Mulkin qananan hukumomi, a lokacin da ta kawo sauye. A wannan lokaci kuwa Jihar Kaduna na qunshe da lardin Zazzau da lardin Katsina. Amma a shekarar 1987 sai aka raba wannan jiha gida biyu, aka qirqiro Jihar Katsina wadda ta qunshi lardin Katsina. Lardin Zazzau kuma ta zama Jihar Kaduna da hedkwalarta a garin Kaduna.

A shekarar 1989/1990, gwamnan Mulkin joja na Jihar Kaduna Mai girma Kanar Abdullahi Sarki Mukhtar, bayan ya yi nazarin matsayin garin Kaduna, sai ya maida ita qarqashin ikon masarautar Zazzau. Saboda dalilan da suka maida ita

---

[1] GTK 20 ga Maris, 1956, shafi na 11

[2] Newscope, *A Kaduna State Government Publication, Vol. 5* No. September 2008, shafi na 30.

hedkwatar Jihar Arewa basu da tasiri a wannan zamani.[1] Daga wannan lokaci ne Kaduna da masarautunta suka koma qarqashin mulkin Sarkin Zazzau.

A nan ya kamata a ba da taqaitaccen tarihin Sarakunan da suka taka rawar gani wajen Sarautar Sabon Gari. Su waxannan shugabanni babu shakka sun nuna qwarewa da gogewa da kuma hangen nesa wajen mulki. A lokacin Sarkin Zazzau Ja'afaru ne aka fidda Kaduna daga qarqashin Zazzau. A lokacin Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris, CFR Kaduna ta qoma qarqashin Zazzau. Sabonda haka ne aka kawo taqaitaccen tarihin Sarakunan wannan lokaci. Duk da cewa an sani sauran Sarakunan Zazzau sun ba da gudunmawarsu wajen havakadda ci gaban wannan gari.

A zamanin Sarkin Zazzau Alu (1903-1920), aka kafa garin Kaduna. Bayan mulkinsa sai Sarkin Zazzau Malam Xalhatn Xan Yero (1920-1924). Daga shi sai Sarkin Zazzau Ibrahim Xan Kwasau (1924-1937) duk waxannan Sarakuna sun taimaka wajem mulkin Kaduna, amma wannan littafi, ba zai kawo taqaitaccen tarihinsu a nan ba. Mulkin Sarakunan Zazzau ya qara qarfi sosai a lokacin varkewar yaqin duniya na Biyu. Wato lokacin Sarkin Zazzau Jafaru. A lokacin sa ne mulkin Sarakunan Zazzau a Kaduna ya samu canje-canje. A zamaninsa ne kuma guguwar neman 'yanci da qungiyoyin siyasa suka fara tasowa. A dalilin haka aka kawo taqaitattun wasu Sarakunan Zazzau daga zamaninsa.

Sarkin Zazzau Jafaru Xan Isyaku

An haifi wannan mashahurin Sarki, kuma Alaramma, sannan malamin Malamai a shekarar 1887. Mahaifinsa Malam Isyaku xa ne ga Sarkin Zazzau Abdullahi Xan Hammada. Ya girma a hannun iyaye da kakanninsa saboda haka ya samu karatu, da tarbiyya kyakkyawa; ya kuma fahinci hulxa da jama'a da sanin makamar mulki tun yana qarami. Wannan horo da ya samu ya yi tasiri sosai a kansa a lokacin da ya zama Sarki.

Malam Ja'afaru ya taso da natsuwa, da hankali, da haquri da kaifin basira wanda Allah Ya huwace masa. Ma'abucin karatu ne kuma mai matuqar son neman . Ya yi karatun Allo a hannun Mahaifinsa da shahararrun malaman Zazzau kuma limaman kona, musamman limamin kona Malam Muhammadu Sani. Kafin ka ce kwabo, abinka da mai maxaukakkiyar daraja har ya hardace Alqur'ani Mai girma ya zama Alaramma. Ga abin da limamin Kona Malam Aliyu Ibrahim ya ce game da wannan mashahurin xalibi: "ya fara karatun Alkur'ani tun yana qarami ya kuma maiyaze karatunsa har ya hardace Alqur'ani a gidan limamin Kona. Yana

[1] Newscope, *A Kaduna State Government Publication, Vol. 5* No. September 2008, shafi na 30.

xaya daga cikin daliban da aka karrama da "Hafizul Qur'an " wato mahardaccin Alqurani.

A wajen fannin ilimi kuma Malam Ja'afaru a nan ma ya sharara a fannoni daban-daban. Ya sharara a *Muhtasaral Halil* (Fiqihu), da *Muqamaitul Harir* (Lugga), da *Tuhufattul Harir* (Sharia), da *Alfiyyatubnu Malik* (Nahawu) da *Lamiyyatul Afal* (Tasrif), da *Aikazal Himan fi – Shahi Hikam* (Falsafa) da *Samarqandi, Muwaxxa Malik*, da *Buhari* (Hadisai). Saboda haka a cikin xan qaramin lokaci sai sunan Malam Jafa'aru ake ji a tsakanin mashahuran malaman Zariya.[1]

Malam Ja'afaru yana xaya daga cikin 'yan Arewa da suka shiga Makarantar Boko ta Farko da ke birnin Kano. An zave shi zuwa wannan makaranta a shekarar 1911, a lokacin yana da shekara ashirin da huxu da haihuwa; Alaramma kuma malami matafannani. Waxanda ya yi zamani da su a wannan makaranta sun haxa da; Bello Kagara (wanda ya zama Walin Katsina), da Adamu Wushishi, da Baba Dankaden Kano, da Muhammadu Yola Kano, da Sulaiman Sarkin Dutse, da Ahmadu Magajin Malam, da Jibril Xan Korau Zariya, da Hassan Sarkin S Bauci, da Abba Kyari (wanda ya zama Shehun Barno), da Mustapha (wanda ya zama Lamixon Adamawa) da Abubakar Umaru.[2]

Da ya kammala karatunsa a shekarar 1912, sai Razdan na Zariya Keftin J.M Fremantle ya xauke shi aiki a matsayin Masinjan gwamnati akan albashin sulai talatin a wata, wannan albashi ne mai tsoka a wancan zamani. Wannan mashahurin malami kuma yarima mai jiran gado ya qarbi wannan muqami yana mai cewa, "Godiya Ta Tabbata Ga Allah, " bai nuna homa da girman kai ba. Ammasu Turawan akwai abun da su ka gani ga wannan bawan Allah da kuma baiwoyinsa iri-iri da ke fitowa fili musamman a wajen shugabanci. Haka kuma sun fahimci irin siyasar da ke akwai a tsakanin Gidajen Sarautar Zazzau. Don haka ba su ba shi wani muqami da zai fito da shi fili sosai ba. Amma a matsayinsa na masinja, zai matso kusa da su har ya koyi harkar mulki irin na zamanin da ke tafe.

Haka kuma a matsayinsa na masinja zai daxa danqon zumunci da ke akwai tsakanin ofishin Razdan da gidan Sarautar Zazzau. Ya yi amfani da wannan matsayi na sa ya kuma kyautatawa wannan masarauta da lardin Zazzau baki xaya. Saboda haka ne zumuncinsa da Sarkin Zazzau Alu Xan Sidi ya yi qarfi sosai. Idan aka fahimci haka, za a a gane dabara da hangen nesan Razdan Fremantle, wanda ya xauki malam Ja'afaru don ya ba shi horon mulki sosai, ya kuma sa shi ya qwarewajen iya harshen turanci fiye da sauran sa'o'insa waxanda suka fito daga

---

[1] Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isyaku: The Great Emir of Zazzau*, shafi na 159 – Zuwa 161.

[2] *Ibid*. shafi na 169

Makarantar Xan Hausa. Kaga ke nan wannan kamar matsayi ne na "Kwalejin Koyan Mulki " ga Malam Jafaru. Wannan horo ya yi tasiri sosai a kansa a harkokin mulkin ba Arewa ba, a Nijeriya baki xaya musamman a lokacin siyasa da gwagwarmaya neman 'yanci.

Wannan haziqin mutum, ya yi amfani da matsayinsa ya san kusan duk Razdantan da ke Nijeriya baki xaya, ya kuma qulla zumunci da su. Babu shakka sunansa ya kai qasar Ingila tun kafin Allah Ya ba shi sarauta. Wannan ya sa koda ya zama Sarki, kusan ace ya fi sauran Sarakuna hulda da Turawa.

Daga wannan muqami na masinja ne sai likkafa tai gaba, ya zama Magatakarda a ofishin Razdan wato "Chief Scribe in the Resident Office of Zaria. " Su kansu Turawan sun amfana da ilimi, basira da hangen nesan wannan bawan Allah. Babu shakka ya taimaka masu wajen ba su shawarwarin yadda za su tafi da mulkin Zazzau da Arewa, ba tare da sun sami wata mishkila ba. Saboda haka Keftin Fremantle zai alfahari da samun Malam Ja'afaru tare da shi.

Malam Ja'afaru ya samu qarin girma inda ya zama Katukan Zazzau, Hakimin Zangon Katab. A ran 29 ga watan Fabrairu 1918. Muqaddashin Razdan na Zariya Mista C.O Migeod ya aikawa Leftanan Gwamna na Jihar Arewa wasiqar wannan naxi, da Sarkin Zazzau Alu Xan Sidi ya yiwa Malam Ja'afaru. Allah Ya ba shi Sarautar Zazzau, a ranar Lahadi 27 ga watan Yunin shekarar 1937.

An yi qasaitaccen bikin naxin sarauta, Gwamna Janar na Nijeriya Sir Bernard Henry Bourdillon ne ya miqa masa Tutocin Shehu Mujaddadi guda biyu, da Wuqar Yanka, da Takobi da Kwafin Alqu'arni rubutun hannu. Ya kuma miqa masa Sandar Girma wato *First Class Staff of Office*.[1]

A zamanin mulkinsa qasar Zazzau ta bunqasa ta kowace fuska. Haka kuma ya taimaka gaya wajen kafa harsashin ci gaban Nijeriya Ta Arewa. Ya kuma lura da mulkin garin Kaduna da bunqasarta. Allah Ya yi masa rasuwa a ranar Jumma'a 21 ga Agustan shekarar 1959. Allah Yaji qansa, ya Rahamsheshi, amin.

Tasirin Malami A Shugabanci

Abin sha'awa ga wannan tarihi na yaqin jihadi da mulkin Fulani a birnin Zazzau. Akwai abubuwa da yawa da tarihin ke karantarwa. Xaya daga cikin waxannan darussa shi ne tashirin malami akan shugabancin jama'a. Har yanzu malamai za su iya ba da jagoranci mai ma'ana da zai kawo ci gaba. Ana nufin malaman da su ka haxa ilimin addini da na sana'a don tafiya da zamani. Wannan haxakar ce za ta ba su qwarewar mulki domin ci gaban jama'a.

Shigar malamai harkar shugabanci tana da amfani masu yawa sosai. Tana kuma da tasiri mai kyau ga ci gaban al'umma da kuma buwayarta, kamar yadda

---

[1] Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isyaku: The Great Emir of Zazzau*, shafi na shafi na 248

tarihin Sarakunan Zazzau ya karantar. Malamai su ne fitilun al'umma, kuma shugabanni ne masu kawo ci gaban jama'arsu. Malami ne ya san Allah. Ya kuma san haqqoqin da suke tsakanin Allah da bayaninsu. Haka kuma ya san haqqoqin da suke a tsakanin jama'a wajen hulda da junansu. Su ne kuma suka xora jama'a a bisa mulkin da ke dacewa da kowane zamani, wato shugabanci bisa kan shari'ar musulunci.

A matsayinsu na malamai suna nuna adalci wajen shugabanci. Suna kuma ba ilimi matsayinsa, suna kuma fifita shi. Ilimi ya samu kafuwa sosai a birnin Zariya saboda tasirin mulkin waxannan malamai Sarakuna. Su ne suka kafa harsashin da ya maida Zariya qasaitaccen birni kuma mavuvvugin ilimi da ya yi suna a duniya. Hasalima Farfesa Abdullahi Mahdi, Shugaban Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya, ya jaddada tasirin mulkin Sarakunan Zazzau a kan yaxuwar ilimi a Arewacin Nijeriya. A lokacin jawabinsa a wajen qaddamar da littafin Sarkin Zazzau, Dokta Shehu Idris, CFR da aka yi a gidan Sardauna wato "Arewa House. Ya ce Sarakunan Zazzau sun ba da taimako gaya wajen yaxa ilimin Allo da ilimin Boko a qasar Zazzau. "[1]

Zariya ta yi suna wajen harkar ilimi a Arewa. Akwai unguwanni masu yawa a cikin wannan birni waxanda suke sanannu ne wajen yaxa ilimin Addinin musulunci kamar Limanci Kona, da unguwar Juma da Kusfa da Bakin Kasuwa. Harkar mulki tana xaya daga cikin dalilin da suka birnin Zariya yin suna wajen ilimi da kuma bashi muhimmancin gaske. Tun daga kafa Daular Usumaniyya, shugabanninta sun yi qoqarin haxa dangartakar ilimi da shugabanci ta qut-da-qut don haka ne Mujaddadi yaba da umarnin Malami shi ne shugaba. Birnin Zazzau na xaya daga cikin qasashen da suka xauki wannan umarni hannu bibbiyu suka kuma bashi muhimmanci ainun.

Akwai misalai masu yawa a tarihin Zariya da ke nuna muhimmanci malami a shugabanci. Alal misali, bayan rasuwar Sarkin Zazzau Malam Musa Bamalle, sai Sakkwato cibiyar Daular Usumaniyya ta naxa Malam Yamusa Babarbare saboda shi ne yafi dacewa saboda fifikon ilimi, duk da cewa a bisa al'ada xansa Malam Sidi Abdilqadir ne ya kamata ya gaji sarauta. A lokacin da Sarkin Zazzau Malam Yamusa ya rasu, Malam Abdulkarim Bakatsine ne ya gaje shi saboda shi ne ya fi ilimi, sai aka naxa shi Sarauta. Shi kuma a lokacin rasuwarsa babu mai ilimin Malam Alu Xan Sidi daga Gidan Mallawa a fannin ilimi saboda haka sai aka naxa shi Sarki. Amma a lokacin da aka tuve shi daga sarauta a shekarar 1922 bai kaucewa tsarin limaminku Sarkinku ba sai ya ba da sunan Malam Abdussalam

---

[1] Ya yi wannan bayani ne, a ran bikin qaddamar littafi; Alhaji Shehu Idris CFR: The 18th Fulani emir of Zazzau, a Arewa House Kaduna, ran 12 ga Mayu 2001.

Basulluve a matsayin mai gadonsa saboda shi yafi kowa ilimi a cikin masu neman sarautar Zazzau.[1]

Malami a harkar shugabanci yana da tasiri mai kyau saboda ya kan ba da shugabanci da adalci ya kuma xaukaka darajar ilimi da Ibada da sana'u. Zariya ta zama tushen ilimi babba a wannan qasa saboda malami mai ilimi shike Sarki, saboda karvuwar ilimi ga Sarakunan Zazzau ne, ilimi ya havaka sosai har birnin Zariya ya yiwa sauran birane zarra a wannan fage.

Farfesa Mahdi masanin tarihi ne ya yi nuni da gudunmawar Sarakunan Zazzau a wajen yaxa ilimi wanda ba kamarsa a Arewa. Haka kuma koda ilimin boko ya shigo, Sarakunan sun karve shi da hannu bibbiyu sun kuma taimaka gaya a wajen yaxa shi. Wannan dalili ne ya sa har yanzu Zariya, a gaba take wajen yaxa ilimin addini da na sana'a.

Ka ga ke nan, malamai ne ya kamata su zama shugabanni, in ana son ci gaban jama'a. Don za a samu adalci wajen shugabanci. Amma idan kazgi ya zama shugaba saboda qwarewarsa a wajen wasu fannoni harkar rayuwa kawai, kamar ilimin Tattalin Arziqi (Economics); Fannin shari'a (law) ko fannin likita (medicine) da sauransu in ba shi da horon ilimin addini, to, babu shakka zalunci zai katutu a sha'anin mulkinsa. Don shi mai ilimi ne a falle xaya rak, wato ilimin duniya. Idan a na son mulki na adalci ya dawo, to ya zama tilas a dawo kan turbar da Mujaddadi ya xora Arewa akai wato "Malamanku shugabanninku. " A nan, ana nufin malamai masu ilimin addini da na zamani masu ilimin Ainihi da ilimin kifaya. Wato mai a falle biyu, na duniya da na lahira. Ko da yake mutum ajizi ne, amma ko shakka babu mulkin malamai zai fi tasiri mai kyau fiye da mulkin kazgi ko mishiriki kowani mai zunzurutun ilimin zamani kawai. Domin shi duniyar ya sani, ita kuma ya sa a gaba da nema ta kowane hali.

Idan mu ka dawo kan Sarkin Zazzau Jafaru akwai abubuwan da rayuwar wannan Sarki ke karantarwa masu yawa. Sarkin Zazzau Jafaru ya xora rayuwarsa a kan Alkur'ani da Sunnah ne. Ya taso yana mai bin iyayensa sau da qafa; tare da neman ilimi mai zurfi na kuma fannoni iri-iri. Ilimin Alqurani Mai girma ya yi tasiri a kansa sosai, shi ne ya buxe masa qirji ya wasa masa kwakwalwa ya kuma bashi kaifin basira. Saboda haka ne ya sami sauqin faxaxa iliminsa cikin hanzari ta kuma fannoni masu yawa.

Saboda ilimi mai zurfi da kyawawan Tarbiyyar da ya samu, sai ya zama mutum mai sauqin kai mara nuna qyama ko fifiko ga kowa. Wannan ya sa ya samu karvuwa ga jama'arsa Musulmi da sauran qabilun waxanda ba Musulmi ba da ke zaune a lardin Zazzau. Jama'a suna qaunarsa sosai saboda adalcinsa. Duk waxannan halaye da wasu makamantansu sun samu ne saboda tasirin malamta a kansa.

---

[1] *History of the Ahmadu Bello University*, ABU Press (1989), shafi na . 26-27

Malam Jafa'aru ya nuna mana cewa rayuwa mai albarka takan fara ne daga qasa, sai ta yi sama. Domin kuwa idan aka faro rayuwa daga sama takan tavavvare ta rushe tai qasa. A matsayinsa na malami mashahuri kuma jikan Sarkin Zazzau, ai matsayin masinja ya yi masa kaxan. Amma sai ya qarvi wannan matsayi cikin farin ciki da godiyar Ubangiji. Qwamfa! Sai ga shi ya zama wani mashahurin Sarki a Afirka. Haka kuma ya nuna mana rayuwa mai kyau, ta yadda da qaddara da aiki tuquru da kuma godiya ga Ubangiji ga dukkan al'amari. Haka Sarakunan Zazzau suka yi mulki a matsayinsu na malamai kuma Sarakuna. Don haka ne wannan babban lardi yaci gaba da bunqasa to kowace fuska har yanzu.

Daga qarshe shugabancin Malam Ja'afaru ya nuna mana tasirin Malami, a sha'anin mulki mai kyau ne. A duk inda malami yake aiki zai iya ba da kyakkyawar gudunmawar ci gaban jama'arsa. Ya kamata Malamai kuma masana su riqa shiga harkokin jama'a suna ba da jagoranci mai kyau. Dalili kuwa tasirantuwar Alqur'ani a kan malami zai ba shi damar qwarewa ta kowace fuskar ci gaban xan-Adam. Saboda haka Malami bai kamata ya taqaita gudunmawarsa wajen ba da *hamsus Salawatu* ba, a'a ya faxaxa idan da hali. Saboda Alku'rani Littafi ne da ke bayani akan komai na sha'anin duniya da lahira. Don haka duk inda malami ya sa gabansa zai yi fice. Dalilin haka ne malaman farko, a tarihin musulunci suka buwaya a fannonin Kimiyya da Fasaha, da ilimin Sararin Samaniya (Astronomy) da lissafi (Mathematics) da (Physics) da (Chemistry) da makamantansu. Don tasirin Alqur'ani a kansu sai suka zama malaman Turawan na farko a fannonin ilimin ci gaban duniya.

Magajin Gari Muhammadu Sambo

Malam Muhammadu Aminu Sambo M.B.E., O.B.E., an haifi wannan mashahurin mutum, gwanin mulki a shekarar 1888, kuma jika ne ga Malam Musa Bamalle, Sarkin Zazzau na farko a mulkin Fulani, wanda ya kafa gidan Sarautar Mallawa. Da ya kamalla karatun Alqur'ani, sai aka sa shi makarantar boko. Yana xaya daga cikin rukunin 'yan Arewa na farko da suka shiga makarantar boko. Ya shiga *Provincial School* ta Kano a shekarar 1908.

Malam Sambo ya gama wannan makaranta ke nan, sai ya zama Shugaban Makarantar *Provincial School* ta Zariya a matsayin "Headmaster. " Wannan makaranta ce ta zama Kwalejin Alhudahuda a yanzu. Saboda Allah Ya yi shi da qwazo da kaifin basira, sai ga shi ya zama shugaban makarantar Midil ta Bauci daga shekarar 1910 zuwa 1916. Saboda haka ya goge a wajen sha'anin yaxa ilimi qwarai da gaske.

A dalilin haka ne sai Sarkin Zazzau Alu Xan Sidi ya naxa shi Hakimin Jaji a shekarar 1916. Wato kamar ance ya dawo shugabanci abin da yake gadon gidansu ke nan. A wannan fanni na mulki, ya nuna qwarewa matuqar gaske. Tun a wancan zamani ya fara gina Gidan Baqi wato *Guest House* a garin Jaji a shekarar 1954.

Wannan gidan ne ya bunqasa, har ya zama 'Babbar Kwalejin Soja' wato *Command and Staff College* Jaji. A shekarar 1937 aka maida shi Hakimin Sabon Garin Zariya. A wannan lokaci ya kafa unguwanni guda biyu: unguwar Muciya da Dogon-Bauci.

Amma bai daxe a kan wannan mulki ba, sai a zamanin Sarkin Zazzau Ja'afaru Xan Isyaku ya maida shi Kaduna, a muqamin Hakimi kuma Magajin Gari. Abinka da mai maxaukakkiyar daraja, hawansa wannan muqami ke da wuya sai nan da nan ya fara bunqasa wannan gari. Wannan abu ya baiwa Turawan Mulki mamaki da ban sha'awa.

A lokacinsa an shiga samun qarin unguwanni da bunqasar wasunsu a garin Kaduna. Kamar bunqasar su: Tudun-Wada, da Unguwar Shanu, da Unguwar Sunusi, da Abakpa, da Kakuri Gwari, da Tudun-Nufawa. Amma bai tsaya a bunqasa unguwanni kawai ba, sai ya shigo Sabon Gari inda yaci gaba da vunqasa wannan gari.[1]

Malam Aminu Sambo ne ya qara tsarin Sabon Garin Kaduna, ya kuma yi qarin manyan titunan: "Sardauna Crescent ", da titin Maiduguri, da titin Bakori, da titin "Constitution. " Shi ne kuma ya qara qawata garin da shuka itatuwa a wuraren da suka dace, a cikin gari. Saboda ayyukansa na ci gaban jama'a tare da qwarewar mulki, sai Sarkin Ingila George, ya karramashi da takardar shaidar girmamawa wato *Certificate of Honour*, a shekarar 1948.

Wannan babbar shaidar yabo sai ta qara ma sa qaimi, ya kuma himmatu wajen vude makarantu. Ya gina makarantar a Tudun-Wada a shekarar 1940 da makarantar titin Maiduguri a shekarar 1958 da makarantar Sabon Gari a shekarar 1961. Waxannan makarantun Firamare, sun taimaka gaya wajen bunqasar ilimi a garin Kaduna.

A shekarar 1956, wannan mashahurin Malami, shugaba kuma basarake ya samu qarin girma, ya zama shugaban Kantoman Hukumar Kaduna wato "Administrator of the Kaduna *Local Authority Government*, " kuma Hakimin Sabon Garin. Shi ne xan qasa na farko da ya fara riqe wannan babban muqami. gwamnatin Ingila ta karrama shi da *Member of the British Empire* (MBE) a shekarar 1954. Ta kuma ba shi ta O.B.E a shekarar 1956.

Sarkin Sabon Gari Malam Baqo

Malam Baqo Ibrahim mutumin Argungun ne ta qasar kabi. An haife shi wajen shekarar 1878. Lokacin da Turawa suka zo Argungu, sai Sarkin Argungun ya ba su yaron da zai taimake su ya kuma nuna masu hanyar da za su fita qasarsa.

---

[1] Hira da Alqali Sa'idu Muhammad da Alhaji Isyaku Na Magajin Gari, ran 1 ga Disamba 1984.

Wanda Sarkin ya ba su kuwa shi ne Malam Baqo. Amma daga baya sai Turawan suka roqi a bar masu shi ya yi masu yaron doki.

Malam Baqo na yi wa Turawan aikace-aikacen dawa kansu, sai suka lura da basirarsa da qwazonsa har suka umarce shi da shiga aikin xan sanda. Ya shiga aikin xan sanda a Sakkwato a ranar biyar ga watan Oktoban shekarar 1903 (5/10/1903). Ya yi shekaru talatin da huxu da wata biyar da kwana ashirin da shida yana aikin Xan Sanda.

A cikin waxannan shekaru da wannan gwarzo ya yi yana aikin Sarki, ya nuna bajinta qwarai da gaske cikin shekara guda da kama aiki har ya samu girman saje. Ya samu muqamin samanja a ranar 1 ga watan Yunin shekarar 1907 a garin Dungurun. Yana xaya daga cikin manya 'yan kaiwa da komowa wajen kafa garin Kaduna. Yana cikin muqamin Samanja ne aka taso daga Dungurun zuwa Kaduna. A ranar 1 ga watan Yulin shekarar 1914 ya zama Saje-Manjo, ya qara samun girma zuwa Rejimanci wato Regimental Sergeant Major ranar 10 ga watan Janairun shekarar 1915.

Rejimanci Malam Baqo, saboda qwarewarsa da basira da himmar da Allah Ya ba shi, sai ya samu qarin girma zuwa, *Major Instructor*, wato Samanja mai koyar da 'yan Sanda. Aikin horar da 'yan Sanda yake yi har ya zuwa shekarar 1938 inda ya yi ritaya a ranar 31 ga watan Maris na wannan shekara.

Ban da bajintar da ya nuna wajen aikin xan sanda, tun farko Allah Ya yi shi mutum ne ma'abucin karatu. Bai daxe da zama da Turawa ba, sai ga shi ya iya rubutu da karatu da aiki da keken rubutu. Hidimomin aikin Sarki ba su hana wannan bawan Allah neman ilimi ba, a cikin shekarar 1920 ne Malam Baqo ke hawa keke ya bi ta unguwar lebura ya tafi garin Kangiwa wajen Malam Hurdi inda yake xaukar karatu. Shi ba wajen Malam Hurdi yake xaukar karatu kawai ba, a'a ya dangana da Malamai da dama Malam Baqo ya karanci fannoni daban-daban.[1]

Irin wannan jurewar neman ilimi na wannan bawan Allah, abu ne mai wuya matuqa idan aka yi la'akari da yadda ayyukan jama'a ke gaban duk wani mai muqamin aikin Sarki. Baya ga haka, ba ya jin qyashin fitar da kuxinsa ya sayi littattafai iri-iri, tun a wancan zamani. Sai ga shi cikin xan qaramin lokaci ya tara littattafai iri-iri masu yawa, wanda duk garin ba shi da na biyu.

Allah Ya yi wa Malam Baqo dauriyar karatu da baiwar ilimi zunzurutu. A lokacinsa ya karanci fannoni daban-daban, ya zama Malami ma ta fannani. Saboda tsagwaron ilimin da Allah Ya ba shi, sai natsuwarsa da kwarjininsa kullum qaruwa suke yi.

Kafin ritayar wannan babban Malami daga aikin xan sanda, sai da ya samu lambobin girma daban-daban waxanda Turawa suka ba shi saboda bajintar da ya

[1] Hira da Alhaji Usman Gwanki ran 29 ga Nuwamba 1984.

nuna. (i) 'African General Service' (ii) 'African Police Medal' (iii) '1936 Jubilee Medal and Colonial Police and Fire Brigade holding Service and Good Conduct with two bars'.

Bayan da ya yi ritaya daga aikin Sarki, wato aikin gwamnati sai aka naxa shi Shugaban, kotun Haxin-Gambiza wato *President Mixed Court* a cikin watan Mayu na shekarar 1940. A lokacinsa ne wannan kotu ta bunqasa sosai. Nan da nan sai Malam Baqo ya yi amfani da iliminsa wajen tafiyar da ragamar alqalancin jama'a.

Saboda girmamawa da darajar da mutanen garin Doka da kewaye ke bai wa Malam Baqo bisa rikon gaskiyarsa, shi ya daxa bunqasar da "Mixed Court. " Kantoman wannan lokaci, Mista McCallum shi da kansa sai da ya ce "kwarjini, bunqasa da havakar wannan kotu a idon jama'ar Kaduna sun samu ne saboda shugabancin Malam Baqo, wanda yake nuna gaskiya da riqon amana wajen tafiyar da sha'anin wannan kotu. "

Malam Baqo yana shugaban Alqalan 'Mixed Court' sai aka naxa shi Sarkin Sabon Garin Kaduna, jin kaxan bayan Magaji Muhammadu Sambo ya samu qarin girma. Sarkin Zazzau Jafaru ne ya naxa shi sarautar a Zariya, muqamin da ya riqe ke nan har ranar 1 ga watan Afrilu na shekarar 1956.

Idan mutum ya dubi yadda wannan bawan Allah Ya haxa tafiyar da shugabancin jama'a tare da neman ilimi da kuma yadda ya yi rawar gani a aikinsa, sai mutum ya yi mamaki, amma babu mamaki ga baiwar Allah. Wannan barden Arewa, qwararren xan Sanda, Babban Malami, Alqali kuma Basarake, ya rasu a cikin shekarar 1968. Ya bar 'ya'ya bakwai, su ne:- Amadu Arugungu (Xan Boyi), da Audu Baqo, da Mairamu (Kurundu), da Balarabe Baqo, da Sani Baqo, da Amina da Rabi'u Baqo. Cikin 'ya'yan nasa, Alhaji Audu Baqo shi ne tsohon gwamnan Jihar Kano.

An samu sauye-sauyen mulkin wannan gari bayan rasuwar Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru Xan Isyaku. Wanda ya rasu ranar Jumma'a 21 ga watan Agustan shekarar 1959 da misalin qarfe 2:35 pm. Da rasuwar wannan Sarki ne sai Alhaji Muhammadu Aminu ya hau gadon Sarauta Sarkin Zazzau Aminu.

Sarkin Zazzau Muhammadu Aminu

Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu shi ne Sarki na goma sha-bakwai a mulkin Fulani. An haife shi a shekarar 1908. Ya samu tarbiyya da karatu irin ta 'ya'yan sarauta. Shi jikan Iya Usman xan Sarkin Zazzau Abdukarim ne. Ya zama Sarki na uku daga gidan Sarautar Katsinawa a Masarautar Zazzau.[1] Malam Abubakar Kwasau xan Iya Usman shi ne mahaifin wannan qasaitaccen Sarki, wato hula biyu ce ke tsakaninsa da Sarkin Zazzau Abdulkarim. A wajen uwa

[1] Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isyaku*, shafi na 63

kuma, shi jikan Sarkin Zazzau Sambo ne, ta nan wajen kuma hula uku ce tsakaninsa da Sarki Abdulkarim.[1]

Bayan da ya gama karatu a *Provincial School* ta Zariya ya shiga aikin En'e ta Zariya a muqamin Dubagari wato Malamin Tsabta a cikin shekarar 1926. A shekarar 1931 ya zama Sarkin Tsabta, muqamin da ya riqe har zuwa shekarar 1938. Malam Muhammadu Aminu ya samu qarin girma, a inda aka naxa shi Sarkin Sabon Gari a shekarar 1938. An qara masa da muqamin shugabancin Mixed Court ta Zariya a shekarar 1940. Likkafarsa ta ci gaba a shekarar 1944 inda ya zama Hakimin Sabon Garin Zariya. Ya qara samun girma da aka naxa shi Iyan Zazzau. Malam Aminu ya samu shekaru ashirin yana riqe da wannan muqamin Sarautar, ya kuma samu karvuwa daga jama'arsa saboda alherinsa.[2]

A ran 29 ga watan Agustan shekarar 1959, aka ba da sanarwar Alhaji Muhammadu Aminu ne Sarkin Zazzau shi ne zai gaji marigayi Sarkin Zazzau Malam Ja'afaru. A ran 30 ga watan Oktoban shekarar 1959, aka yi qasaitaccen bikin tabbatar da Alhaji Muhammadu Aminu ya zama Sarkin Zazzau.

A wannan rana Zariya ta ga qasaitaccen taro wanda aka qiyasce mutane wajen dubu hamsin (50,000) suka hallara a wannan rana ta bikin naxin Sarauta, wanda Gwamna Sir Gawain Bell ya yi. A cikin manyan baqin da suka halarci wannan biki sun haxa da Firimiya Sir Ahmadu Bello, da Ministocin Jihar Arewa, da shugabanni waxanda suka haxa da Sir Abubakar, da Sarkin Kano Sir Muhammadu Sunusi, da Sarakunan Daura, Gumel, Ilorin, Atta na Igala, da Etsu Nupe da Aku na Wukari. Jama'a daga ko'ina sun hallara. Ana jin ba a tava yin irin wannan qasaitaccen taro a tarihin Zariya ba.[3]

An fara bikin da safe. Gwamna Arewa Sir Bell, ya duba faretin da 'yan Sandan En'e ta Zariya suka yi masa, tare da rundunar sojoji 'yan Badujan *Depot Queen's Own Nigeria Regiment* da ke kaxe-kaxe da bushe-bushe, da ya qayatar da wannan faretin ban girma. Daga nan sai Gwamna ya koma can dandamalin manyan baqi, inda ya zauna tare da Firimiya da . Dukkansu suna zaune suna jiran sabon Sarki ya fito a naxa shi.

Da qarfe 9:30 na safe dai-dai sai ga Sabon Sarki nan tafe a bisa ingarman doki, yaci ado na qasaita. Yana sauka daga kan doki sai ya wuce dandamalin manyan baqi, a inda Babban Limamin Zariya ya rantsar da shi. Ana rantsar da shi sai ya xauki alqawarin mulkin jama'arsa da adalci ba tare da son rai ko nuna bambanci ba. Ya kuma ci alwashin tafiyar da aikinsa ba tare da jin tsoro ko son

---

1 Saidu Zango, *Tarihin Sarkin Zazzau M. Aminu*, shafi na 9

2 *Ibid*., shafi na 19

3 *Nigerian Citizen*, No. 780, Asabar, October 31, 1959

zuciya ba. Sabon Sarki na gama xaukar rantsuwa, sai Sir Gawain Bell ya miqe ya gabartar da jawabinsa inda ya ce:

Mai girma Firimiya da Ministoci da sauran jama'a baki xaya. Ina mai matuqar farin ciki da samun damar zuwa nan a yau, domin in yi bikin naxa Alhaji Muhammadu Aminu zama Sarkin Zazzau.

Wato shi ne ya gaji Malam Ja'afaru-Allah Ya gafarta masa, wanda ya yi shekara 22 yana sarautar Zazzau. A wannan lokaci, ya nuna misali naqwarai wajen sha'anin shugabanci da aiki tuquru ga mutanensa da mutanen Jihar Arewa da kuma mutanen Nijeriya baki xaya. Kuma jama'a baki xaya za su daxe suna tunawa da shi saboda waxannan halaye nasa.

Masu naxa Sarkin Zazzau bakinsu ya haxu wajen zaven Alhaji Muhammadu Aminu ya zama Sarkin Zazzau. Ya daxe yana yi wa En'e ta Zariya aiki da gaskiya, musamman dai shekaru fiye da 22 da ya yi yana riqe da muqamin Iyan Gari, wato mai kula da sha'anin mulki a Sabon Garin Zariya. Yadda ya riqe wannan babban muqami har ya yi nasara, ya nuna yadda ya yi aiki da haquri da qwarewa kan sha'anin mulki.

Waxannan kyawawan halaye nasa za su taimaka masa wajen riqe wannan muhimmin nauyi da aka xora masa yanzu wato muqaminsa na Sarkin Zazzau na 17.

Ya Alhaji Muhammadu, wannan zamani fa lokaci ne da ake ta samun canje-canje da ci gaba a fannoni daban-daban. Saboda ilimin da ke ta yaxuwa da kuma gabatowar lokacin samun 'yancin qasar nan, mutanen Jihar Arewa baki xaya suna buqatar aiki tuquru da nuna gaskiya da kuma nuna qwarewa a kowane fanni na aikin gwamnati. Aikinka ne ka tabbatar da cewa Ma'aikatan En'e na Zariya suna tafiyar da ayyukansu yadda ya kamata. Haka nan kuma haqqinka ne tabbatar da cewa mutanen da suka cancanta, kuma masu aiki tuquru su ne kurum aka bai wa aikin En'e. Ni dai nantabbatar da cewa kai da 'Yan Majalisarka za ku ba da misalai na aiki tuquru da rashin nuna son kai da shugabancin qwarai.

Daga abin da ka lura da shi a ayyukan da ka yi tun da farko, tushen kowane irin mulki shi ne kuxi. Saboda haka, ba sai na bayyana irin buqatar da ke akwai ba ta kula sosai da sha'anin kuxaxen En'e. Ya kamata a tsara ayyukan tara kuxin haraji da sauran kuxaxen shiga sosai. Wajibi ne a lura sosai wajen kashe kuxaxen En'e.

Na san cewa babbar manufarka dai ita ce ka kawo ci gaban Qasarka da xan abin da kake da shi, to, amma haka xin ba zai yiwu ba sai tare da lura sosai da sha'anin kuxaxen En'e.

Game da sha'anin mulki kuwa, ikonka ya haxa har da mulkin qabilu dabam masu bambanci addini da al'adun gargajiya. Ina sa ran cewa idan wani rikici ya tashi, za ka yi iyakacin qoqarinka domin ka sasanta yadda kowa zai ji daxi. Zaka lura da muhimmancin bai wa mutane damar tafiyar da ilimin ayyukansu da kansu ta hanyar Majalisun da aka zava. Ina tabbatar maka da cewa za ka sami kowane irin taimako daga jami'an gwamnati na Lardi da kuma Ma'aikatun gwamnati daban-daban. Waxannan Jami'ai za su zo ne musamman domin su riqa bayyana abubuwa, suna ba da shawara, kuma za su riqa taimakonka wajen yin aiki da manufofin Gwanatin Jiha. Ina fatan za ka amince dasu.

Haqiqa wannan baban nauyi ne aka xora maka, amma misalan da Magabatan ka suka bayar, da biyyayar mutane, da kuma cikakken goyon bayan gwamnati, sun isa su baka qwarin gwiwa. Saboda haka, ina mai matuqar farin ciki da miqa maka kayan Sarautarka, wato na naxa ka Sarkin Zazzau da aka yi.

"Ina fatan tare da taimakon Ubangiji za ka yi wa qasarka jagora zuwa ga samun alheri. Allah Ya daxe da zamaninka, ya bai wa Qasar Zazzau ci gaba Amin.[1]

Bayan Gwamna ya gama jawabinsa sai Sarkin ya maida jawabi kamar haka:

'Assalamu alaikum wa rahmatullahi ya jama'a da suka taru a wurin nan yau.

Ni, Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu, na gode wa Allah Maxaukakin Sarki, na yabi AnnabinSa Muhammadu wanda tsira da amincin Allah suka tabbata a gare shi, na gode albarkacin iyaye da kakanni, na gode ma jama'an qasar Zazzau da sauran jama'an da suka taru a nan.

Bayan haka, ina yin maraba ga Mai girma Gwamna, Mai girma Firimiyan Jihar Arewa da Ministoci, Mai girma da Sarakuna da sauran manyan baqi. Ina matuqan farin ciki da godiya gareku da kuka samu damar halartar wannan taro don naxin Sarkin Zazzau a yau. Na tabbata dukanku kuna da manyan ayyuka da alhakukka masu nauyi, amma duk da haka ga shi kun sami ikon zuwa.

---

[1] Sa'idu Zango, *Tarihin Sarkin Zazzau M. Aminu*, shafi na . 31-32

A cikin jawabin Mai girma Gwamna; ya ambata batun yadda aikace-aikacen qasa za su tafi sosai a sami ci gaba kuma da yadda za mu kula da sha'anin kuxaxe da majalisu. Na ji na karva da farin ciki. Na kuma tabbata za mu yi iya kan qoqarinmu mu ga haka ya samu.

Wannan rana 30 ga Oktoban shekarar 1959 babbar rana ce abar tunawa gareni da sauran jama'ar qasar Zazzau don a yau na zama Sarki na 17 na Sarakunan Fulani da suka karvo tutan Raya Addini daga Mujaddadi Shehu Usman. Allah shi yi jinqai gare shi amin.

Wannan kayan amana mai nauyi da aka aza mini, a yau, mai nauyi ne qwarai da gaske. Na sani ko yaushe yana da nauyi, amma kowane zamani da irin nasa nauyin.

Na tabbata wannan kayan amana da aka aza mini, bani da ikon xaukarsa sai da taimakon Ubangiji Allah da taimakon 'yan Majalisa, Hakimai, Dagatai da Ma'aikata, bisa aiki sosai da gaskiya da riqon amana da rashin son kai; har wa yau kuma jama'an qasa sun kula da bin dokoki da umarni.

Ina so in xauki wannan dama da na samu in yi wa jama'a jawabi kan zave mai zuwa. Ina roqon jama'a tun daga yau har ranar da za a jefa quri'a, su tsaya bisa bin dokoki da zama babu yamutsi ko tashin hankali, in haka ya samu kuwa, mun sami abin alfahari ke nan.

Muna fata Allah shi qara wa qasarmu Arewa da Nijeriya baki xaya arziqi da albarka da lafiya da zama lafiya, Amin. Ina fata Gwamna da Firimiya da Sarakuna da sauran manyan baqi da suka samu daman halarta wannan biki Allah shi maisheku gidajenku lafiya, Amin.

Sarkin Zazzau Aminu ya amsa jawabin Gwamna da cewa ko da yake an xora masa nauyin haqqin jama'a a kansa, idan ya samu haxin kan 'yan Majalisarsa da na Ma'aikatan En'e da sauran jama'a, da yardan Allah, zai kai ga nasara wajen sauke wannan babban nauyi da ke wuyansa. Yana gama jawabi sai, Hakimai, da Dagatai, da Ma'aikatan En'e da Kansiloli da sauran jama'a suka riqa zuwa suna yi masa mubayi'a.

Wannan qasaitaccen Sarki wanda ya yi namijin qoqarin bunqasar arziqin qasar Zazzau, zaman lafiya da jin daxin jama'arsa, ya rasu ran 1 ga Janairun shekarar 1975 a Ingila. A lokacin rasuwarsa yana tare da Alhaji Shehu Idris, wanda ya zama Magajinsa.

Sarkin Zazzau Shehu Idris

An haifi wannan qasaitaccen Sarki Alhaji Shehu Idris ran 1 ga Agustan shekarar 1936. An naxa Alhaji Shehu Idris Xanmaxamin Zazzau a ranar xaya ga

watan Maris 1975, ya zama Sarkin Zazzau. Ya gaji marigayi Alhaji Muhammadu Aminu, wanda ya rasu a wani asibiti a London, ranar Talata, 4 ga Fabrairun shekarar 1975. Alhaji Shehu Idris, wanda ya fito daga Gidan Sarautar Katsinawa, xan Malam Auta (1879-1888) ne, wato jikan Malam Sambo ne Sarkin Zazzau na goma a mulkin Fulani.

Bayan rasuwar Sarkin Zazzau Aminu sai aka umurci masu zaven Sarki da su gaggauta yin zave don a samu sabon Sarkin Zazzau. Kwamitin da ke da alhakkin zaven Sarki, yaqunshi mutum biyar ne waxanda suka haxa da: Wazirin Zazzau Nuhu Yahaya, da Fagacin Zazzau Muhammadu, da Makaman Zazzau Haliru, da Limancin Juma'a Muhammadu, da Limancin Kona Balarabe.[1]

A lokacin takarar wannan Sarauta an sami 'yan takara daga kowane gidan Sarauta waxanda suka fito neman wannan muqami. A wannan lokaci kuma Alhaji Shehu Idris shi ne mafi qanqantar shekaru a cikin 'yan takarar neman wannan Sarauta, wanda hakan har ya jawo jayayya a tsakanin masu zaven Sarki dangane da shekarunsa.[2] Amma zaven Allah shi ne zave. Don haka ne ma da Alhaji shehu Idris ya zama Sarki sai ya ce:

> *Wannan matsayi da Allah Ya kaini na Sarkin Zazzau ban tava nema wurin wani ba, babu wani daga cikin masu zaven Sarki wanda na nemi ko nayi masa wani abu don in nemi wannan matsayi. Ni ban nema ba sai mutane masoya sun yi ta nema na da in fito in nemi wannan matsayi lokacin da Allah Ya yi ma Sarkin Zazzau Muhammadu Aminu rasuwa. Allah Ya rubuta cewa nine Sarkin Zazzau, saboda haka masu sona cikin masu zavan Sarki suka ba da suna na a matsayin wanda ya cancanta ya yi sarautar Zazzau, kuma mafi kusanta gareni daga cikin masu zaven Sarkin shi ne Fagachi Muhammadu saboda irin kusanta da soyayya da ke tsakanin su da Sarkin Zazzau Muhammadu Aminu, ban tava ce masa ina da wata buqata ba a tare da ni, na tabbata cewa biyayya da qana'a ke tabbatar da xaukaka ga xan-Adam.*[3]

Wannan sabon Sarki ya cika duk qa'idodin da gwamnati ke buqata ga duk mai neman wannan muqami. Malam Muhammadu Jumare wanda shi ne Wakilin gwamnati ya tabbatar da da cewar wannan xan takara ya dace. Saboda haka sai dacewar gwamnati ta dace da ta masu zaven Sarki. A dalilin haka sai aka ba da

---

1 Abbas M. Fagachi, *Mai martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris CFR*, Sankore Educational Publisher, Zaria (2005), shafi na 86

2 *Ibid*.

3 *Ibid*. shafi na 80

sanarwa cewa Alhaji Shehu Idris ne Allah Ya zava ya zama Sarkin Zazzau, a ranar 8 ga Fabrairun shekarar 1975. An yi bikin naxin sarautarsa a ranar 11 ga Afrilun shekarar 1975. A wannan rana ce gwamnan Jihar Arewa ta Tsakiya, Birgediya Abba Kyari ya miqa masa sanda a gaban Sarakunan Arewa, a matsayin Sarki Mai Daraja ta Xaya, a filin Sukuwa da ke hanyar Samaru a Sabon Garin Zariya.[1]

gwamnan Jihar Arewa ta Tsakiya, Birgediya Abba Kyari, shi ne ya tabbatar da naxinsa a bisa shawarwari Majalisar naxa Sarakuna ta Jihar Arewa ta Tsakiya bayan masu zaven Sarki na gargajiya sun zave shi.

Har zuwa lokacin da aka naxa shi Sarki, Alhaji Shehu Idris shi ne Hakimin Birni da Kewaye, kuma shekarunsa na haihuwa 39 ne. Ya tava riqe matsayin Sakataren Qaramar Hukuma, sa'an nan ya zama Sakataren Sarkin Zazzau na shekara goma kafin a naxa shi ya zama Hakimin Birni a shekarar 1973.

Sabon Sarkin, ya yi karatunsa a Midil ta Zariya, daga nan sai Kwalejin Malamta ta Katsina, inda ya sami satifiket ta koyarwa mai daraja ta uku, daga baya ya halarci Kwas na samun *Diploma* na lissafin kuxin Qananan Hukumomi. Ya yi Kwas na Mulkin Qananan Hukumomi a Makarantar Koyon Mulki ta Zariya.

Har ila yau, Alhaji Shehu, ya halarci Kwas na sha'anin mulki a Australia. Ya riqe muqamai da dama, daga cikinsu har da na Shugaban Makarantar Firamare daga shekarar 1958 zuwa 1960. Ya riqe matsayin babban Akawu a Ma'aikatar Ayyuka ta Qaramar Hukuma daga shekarar 1961 zuwa 1962. Haka nan kuma ya tava riqe matsayin Mataimakin Jama'ar Ofis a qarqashin gwamnati Arewa ta da daga shekarar 1963 zuwa 1964, daga baya kuma ya zama Sakataren Qaramar Hukumar Zariya daga shekarar 1964 zuwa 1973.

Dubban mutane daga dukkan sashen Jihar Arewa ta Tsakiya da maqwabtansu sun tafi Zariya domin yin mubaya'a da sabon Sarki. A lokacin ya yi jawabi ga jama'a, ya bayyana cewa mulkinsa zai kawo sabon mataki ga manufar mulkin Qananan Hukumomi. Sabon Sarkin ya ce zai yi qoqari ya ga an sami ci gaba ta kowane fanni a cikin sashen mulkinsa. Abubuwan da ya fi sha'awa ta fuskar wasanni, su ne qwallon gora, hawan doki da kuma qwallon bango.[2]

Sarautar Zazzau ba mai sauqi ba ce ko kaxan, ta bambanta da sarautar sauran qasashe a Arewa. Saboda akwai ta da arziqin jama'a da qabilu iri-iri. Kuma qabilu daban-daban waxanda suka bambanta a al'adu da addini. Don haka mulkinsu abu ne mai wuya. Hasalima dai, idan Kaduna na cikin masarautar Sarki, tilas ne Sarkin ya zage xantsensa domin yana sarautar wata qaramar Nijeriya ce.

---

[1] Abbas M. Fagachi, *Mai martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris CFR*, Sankore Educational Publisher, Zaria (2005), shafi na 89

[2] GTK Litinin 17 ga Fabrairu 1975.

Amma tun da Sarki Shehu Idris ya hau gadon sarauta yake ta nuna qwarewa a shugabancin jama'a ta nuna adalci, da sauqin kai tare da so da tausayin jama'arsa. Saboda fahimtar waxannan halaye kyawawa, sai jama'arsa suka sallamasa suka bi shi cikin ladabi da biyayya. Allah Ya yi shi mai haquri ne matuqar gaske, gashi kuma baya qyamar kowa. A wajen haqqoqin jama'a kuwa, ba ya nuna bambancin qabila ko na addini. Aqidarsa ita ce a baiwa kowa haqqinsa. Saboda haka a kullum sai jama'a qara son sa suke yi. Ta yaya za mu san yana tare da jama'arsa?

Masana da suka yi bincike a kan Mai martaba Sarkin Zazzau sun ba da tabbacin cewa Allah Ya yi wa Sarkin Zazzau Shehu haquri da zurfin tunani akan yadda zai zauna da kowane irin mutum, ta haka ne ya dushe qazamar gabar sarautar wadda ake da ita a Gidajen masarautar Zazzau. Ya kuma sami yabo wajen kusantar mutane, da hakuri, da Raya Gidajen Sarautar da suka faxi, da kyautata yin Alheri ga jama'a. A kan haka ne Malam Abbas M. Fagachi, ya ce:

"Bari mu fara bayani a kan batun farko, wato kusantar mutane: Allah Ya yi wa Sarkin Zazzau Shehu hikimar jawo mai qinsa ta yadda zai fahimtar da shi rayuwar zaman duniya. Ta haka ne ya sami basira ta gane abin da ke damun jama'a kuma ya san yadda zai yi maganin abin, wanda yin haka, shi ne ke kawo sakamakon shugabanci nagari.

"Haquri:- Allah Ya yi wa Sarkin Zazzau Alhaji Shehu haqurin zama da jama'a. Ya sha gwargwarmaya qwarai a kan harkokin da suka shafi zumunci, mulki, addini, gwamnati da sauransu. Amma saboda haquri, ba ya cewa komai, ko da ana zarginsa da sa hannu a wani abu da ya taso, ba zai ce komai ba har sai abin ya wuce sannan gaskiya ta yi halinta, jama'a su gane ba shi da hannu a abin. Ko da yake shi mulki ya gada, to, amma idan babu haquri sai ka ga ba a cimma nasara ba. To, haka ya yi ta haquri da 'yan'uwa da jama'arsa da Allah Ya xora masa mulkinsu. Haqurin sa ya sa ba ya riqo ga abin da aka yi masa ko aka ce ya aikata. Don haka ne ma ake masa kirari da "Damo Sarkin Haquri Jikan Sambo "[1]

Akwai abubuwa da yawa da za su, nuna mana cewa shi Sarki ne mai jama'a, yana kuma tare da su. Amma za a taqaita da misalai guda biyu. Na farko, a lokacin da ya yi bikin cika shekara ashirin da biyar akan gadon Sarauta wato *Silver Jubilee*, Sarkin ya kira jama'ar, qasarsa amma sai mutanen Nijeriya suka amsa kiran Sarkin gaba xaya. A wannan rana fadar Zazzau ta ga dafifin jama'a kamar Arfa. Me kuma wannan taro ya nuna? Amsuwa ga jama'a qabilu iri-iri mabiya addini daban-daban ba a lardin Zazzau ba, a Tarayyar Nijeriya baki xaya. Ganin haka ne ma har wasu na cewa Sarkin Zazzau ya tara Nijeriya a faxarsa.

---

[1] Abbas M. Fagachi, *Mai martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris CFR*, shafi na . 114-115.

Na biyu, a lokacin rikice-rikicen Kaduna da suka kusan wargaza Nijeriya, Alhaji Shehu Idris ya nuna wata karama. Hargitsin siyasa da qabilanci da na addini da kuma na talauci sun cakuxe, suka kuma cinna wutar fitinu da suka haddasa kashe-kashen jama'a da asarar dukiya mai yawa. A qarshen shekarar 2001 da farkon shekarar 2002 an tafka faxa tsakanin Musulmi da Kirista mazauna Kaduna. Wani irin bala'i ne ya faxa wa mazauna wannan gari, wanda sai da aka sa sojoji a ka kuma ba su iznin harbi, kafin a shawo kan wannan hargitsin da aka baiwa sunan "rikicin addini. " Kaduna kuma qaramar Nijeriya ce, an ce in ta tashi da mura sai qasar ta tashi da zazzavi. Saboda haka hankalin kowa ya tashi.

To, ana qoqarin kwantar da tarzoma a Kaduna sai ga ta Zariya za ta tashi. Don kuwa sai ga Musulmi da sta da ke Zariya sun fito kowa xauke da manyan makamai za a a gwabza faxan addini. To, Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris na cikin gidansa sai ga mummunar labari, an ce da shi, "Ranka ya daxe, yau Musulmi da sta za su gwabza yaqin addini a Zariya, " kafin ka ce me, sai Sarki ya fito daga gida a guje, ko rawani bai xaura ba, yana gudu yana sarsarfa, sai gashi kwatsam! a tsakiyar filin daga. Ya kira jama'arsa, ya ce da su ku bar faxa kowa ya kom Kirista a gida.

Allahu Akbar! A wannan lokaci da hargitsi ya kai tsanani na inna-naha, hankula kuma suka kusa su gushewa jama'ar Musulmi da Kirista, sai aka ga "fagen yaqi " ya yi tsit, jikin mayaqa kuma ya yi sanyi. Kowa sai yanatsu ya koma gidansa. Kai ka ce wuta ce Sarki ya kwarawa ruwa. Kan ka ce kwabo kowa ya watse. Jama'a kuma sun koma gida, kowa ya ci gaba da hada-hadarsa kamar yadda aka saba.

Mu da muka ga abin da da ake kira hargitsin addini a Kaduna, abin da ko sojoji na fargabarsa sai muka ji abin da Sarkin Zazzau ya yi wajen kwantar da wannan bala'i wani nuna jaruntaka ne da karvuwa ga jamararsa, sai muka qara godiya ga Allah da Ya azurtamu da wannan Sarki mai adalci, muka yi kuma salati ga Manzonsa, saboda nasarar da Allah Ya bayar wajen kwantar da wannan tarzoma. A wannan lokaci mai haxarin gaske sai gashi Sarki Shehu Idris ya nuna rashin tsoro tare da so da kishin jama'ar. Saboda haka ne ya sadaukar da ransa a wannan rana.

Sarkin ya nuna gayar jaruntaka a lokacin tasowar wannan hargitsi, wanda ya cancanci yabo. Irin wannan hali ne, Sarkin Bauci Malam Adamu Jumba ya nuna har Gwamna Janar ya ba shi Lambar Jaruntaka, a watan Fabrairu na shekarar 1960. A wancan lokaci dai wani mummunan hargitsi ne ya taso a lokacin da Sayawa suka tada wani hankali na tawaye a Tafawa Valewa Qasar Ajiyan Bauci. Amma himmar Sarkin Bauci sai ya sa wuta ta lafa ba a zubar da jini ba. A dalilin haka ne Sarauniyar Ingila ta aiko masa da lambar jaruntaka, wanda Gwamna Janar, Sir Robertson ya maqala wa wannan Sarki, a wani qasaitaccen biki da aka

yi, wajen ba da wannan muhimmiyar kyauta. Sarkin ya sami wannan lamba da Di'on Bauci Mr. Terner, wanda tare suka kashe wutar.[1]

Irin wannan hali ne Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris, CFR, ya nuna a lokacin da baqin haxarin "Rikicin Hargitsin Addini " zai varke da ruwan kashe-kashe a Birnin Zazzau. Irin wannan hali na jaruntaka da kuma nuna karvuwar jama'arsa, sun sa mun tafi takanas don mu yi godiya ga wannan qasaitaccen Sarki.

Kashe gari da aukuwar wannan abu mai ban al'ajabi sai na tafi wajen Sarki a matsayi na xaya daga cikin dagatansa don in yi godiya ta musamman. Nace, "Mai martaba, mun gode Allah, ai ba Zariya ka ceta ba, Nijeriya ka ceta baki xaya. " Sai Mai martaba ya ce: "Alhamdulillahi, wannan hargitsi ya kwanta. Mu na qoqarin kwantarda tarzomar Kaduna za mu ci gaba da yin qoqarinmu, mu ga cewa bai vullo ba a Zariya ba a ko'ina. Domin idan rikicin ya vullo a Zariya zai qara muni sosai. Mun gode Allah. A ci gaba da kiran jama'a da su zauna lafiya da junansu. Babu addinin da ya yarda da irin wannan kashe-kashe.

A duk lokacin da hargitsi ya yi qamari, mutane kan sami zarmewar hankali. A wannan lokaci ba sa sauroron kowai sai sun aikata abin da suka fusata akai, kafin su huce haushinsu. A shiga cikinsu a wannan lokaci abu ne mai haxari sosai. Don kuwa wani daga nesa na iya wa mutum mummuna rauni ba kuma za a ganshi ba ballanta a kama shi. Idan da Zariya ta shiga cikin rikicin addini a wancan lokaci da ko shakka babu Kano jalla babbar Hausa ita ma sai ta shiga. Allah Ya kiyayi da Nijeriya ta samu kanta a wani mummunan hali na rikicin addini wanda ka iya wargaza ta.

A zamanin wannan Sarki ne garin Kaduna ya koma qarqashin Sarautar Zazzau. A shekarar 1988, a lokacin gwamnan Mulkin Soja na Jihar Kaduna Kanar Sarki Abdullahi Mukhtar ne Kaduna ta sake komowa qarqashin mulkin Zazzau bayan da aka vulguce ta a shekarar 1956. A dalilin haka ne Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris CFR, ya sake fasalin masarautun garin Kaduna. Tun daga wannan lokaci ake samun sahalewar jama'ar Kaduna da gidan Sarautar Zazzau. Wannan nasara ce babba da Zazzau ta samu a zamanin "Balaraben Sarki Jikan Sambo. "

Havakar Sabon Gari

Kafa wannan gari na Kaduna da leburori da tsofafin sojoji qarqashin Gwamna Lugga ya dace da shugabanni masu qwazo da nagarta sosai. Wannan ne ya sa Tura

wan mulki suka samu damar tafiyar da sha'aninsu cikin lumana da zaman lafiya. Dokokin da suka tsara su masun haifar da bunqasar garin qwarai da gaske. Cikin hanzari sai jama'a suka riqa bankowa garin har ya cika maqil.

---

[1] GTK 12 ga Fabrairu 1960

Kyakkyawan tsarin da aka yi wa garin da fasali mai kyau sun taimaka wajen jawo hankulan jama'a zuwa wannan gari, wannan shiri na Gwamna Lugga wanda tun fil azal yake son maida wannan gari hedkwatar Nijeriya baki xaya.

Zaman Kaduna a matsayin hedkwatar lardunan Arewa, ya turo ma'aikata daga garuruwa daban-daban zuwa wannan gari, saboda haka ma'aikata ba qaramin bunqasa Kaduna suka yi ba. 'yan kasuwa, 'yan makaranta da dai sauransu sun zo wannan gari a xan qaramin lokaci.

Tun cikin shekarar 1913, Turawa 'yan kasuwancin Kamfanin "Royal Niger " wanda ya zama kamfanin *United African Company* (U.A.C), sun buxe shagunan kasuwanci a garin Kaduna. Tun ma kafin wannan lokaci, waxannan 'yan kasuwa sun buxe kasuwar suna cinikin Fatu da Qoqon Qwara da gyaxa, a hankali kuma sai kamfanoninsu suka shiga bunqasa.

Waxannan 'yan kasuwar sun taimaka wajen bunqasar arziqin 'yan kasuwa 'yan qasa. A cikin 'yan kwangilar kasuwanci da wannan babban Kamfani, akwai wata Banufiya mai suna Inna Kashie (ko Kashie Kano) wadda tayi suna a Arewa. Arziqin wannan mace ya bunqasa sosai wajen aikin kwangila da kamfanin U.A.C. Inna Kashie ita cewadda ta fara mallakar motar shiga a garin Kaduna a wajen shekarar 1924. Daga Inna Kashie sai Sarkin Pawa Muhammadu wanda ya sayi motar Muhammadu Tambari a cikin shekarar 1931.

Saboda havakar arziqin mutanen Kaduna, sai jama'a suka riqa sayen motocin shiga a wannan zamani. Cikin xan qaramin lokaci waxanda suka mallaki motocin shiga su ne; Mista Thompson da Mista Olajide da kuma Lawal Xan Sarkin Mutane da Malam Xahiru Mai Noma da Isa Wali da Umaru Hofa da Ladan Hunquyi.

Waxanda suka fara mallakar motocin haya da suke zirga-zirga tsakanin Garin Doka zuwa Maqera a kan kuxi 2d su ne: Mai Buruji da Mista Robert da Fafunfafun (Sunan da direban motar ya samu saboda hon xin motarsa). Amma zirga-zirgar mota daga Kaduna zuwa Zariya a motar haya ana yi a kan sule da sisi, wanda ya fara mallakar motar hayar da ke bin wannan hanyar wani qwara ne mai suna Shaban.

Wajen sharholiya kuwa, wasu matan sojoji ne da ke dafa giyar sayarwa, suka buxe wajen shan giya. Saboda haka da cewa la'asar sakaliya ta yi, sai mashaya giya su tafi wajejen sayar da giya su ba da 'yan kwabbansu a ba su su sha su yi tatul. Mutanen wannan gari ba su san Otal ba sai zuwan wani Ibo mai suna Mista Green. Shi ne mutum na farko da ya fara buxe Otal a garin Kaduna. Shi wannan Ibo ya auri wata Bakanuwa mai suna Binta, don haka ake ce da shi Mista Green Na Binta. Tun cikin shekarar 1920 ake yin wasannin Golf da Tennis da Cricket a kulob xin wasanni na Kaduna.

Duk inda Turawa suke yana daga cikin halayyarsu idan lokacin aiki ya yi sai a tsaya a duqufa wajen aiki. Haka kuma idan ka gansu suna hutawa sai ka ce ban da

hutu ba abin da suka iya. Turawan mulkin tun a wajen shekarar 1920 sun haxa kulob a Kaduna domin wasanni iri-iri. Kowane xan kulob yana biyan sulai biyar (5s) a kowane wata. Ana wasan qwallon Tennis da Golf da na Cricket. Akwai kuma wasan Polo, 'yan kulob xin Polo suna wasanninsu da Yammar ranakun Litinin da Laraba da kuma Juma'a tun cikin shekarar 1920.

Qungiyar Al'ummar Kaduna

Jama'ar Garin Kaduna suna zaune ba tare da nuna bambancin addini ko na qabila ba. An kafa qungiyoyi masu yawa don samun havaka a lokaci daban-daban. Qungiyar farko ita ce qungiyar Al'ummar Kaduna wadda aka kafa tun wajen shekarar 1920, shugabannin wannan qungiya mai suna qungiyar Al'ummar Kaduna wato *Kaduna Community League* su ne: Malam Mai Buruji, da Korori Xan Malam, da Mista Ladipo, da Mista D.I. Imoudu, da Babbar Riga, da Malam Rafa, da Namarashe, da Malam M.A. Inuwa, da Mista Nwanko. Sauran qungiyoyin da aka kafa a wannan lokaci har da Qungiyar Ma su Gidaje da 'yan Haya wadda za ta tabbatar da zaman lumana tsakanin mai gida da 'yan hayarsa. Vullowar waxannan qungiyoyi a a lokuta daban-daban alama ce da ke nuna zaman lafiya da sahalewar junar a jama'ar Kaduna.

Daga baya an samu qungiyoyi masu dama da suka vullo kamar: qungiyar 'yan Mata, shugabannin qungiyar su ne: Hajiya Katiti, da Hajiya Ramatun Buda, da Kari da Gwado, da Hajiya Tinka. Wajen masu Wasan Kwaikwayo kuwa akwai Mamuda Gwamna, da Alhaji Bala Keffi, da Alhaji Bala I.G.P. da Alhaji Yaro Tela da Nadada Tela.

Taron qungiyoyin Al'ummar Siyasa daban-daban ya yi tasiri akan mutanen garin Kaduna. A lokacin da guguwar siyasa ke kaxawa a Arewa, sai jama'ar wannan gari suka ga lokaci ya yi, da za a dama da su a harkokin siyasa. Akwai 'yan siyasa da jam'iyyun siyasa da yawa a garin Kaduna, akwai 'yan jam'iyyar NPC, da NEPU, da NCNC da sauran jam'iyyun Qabilu. Saboda 'yan wannan gari su yi tasiri a waxannan jam'iyyu sai suka ga amfanin kafa qungiyar Al'ummar Kaduna wadda za ta taimaka wajen raya gari da jin daxin Jama'a.

A shekarar 1952 aka yi babban taro a *Green Hotel*, a wani qasaitaccen bikin qaddamar da wannan qungiya Kaduna Community League da aka yi a garin Kaduna. An ce mutane wajen dubu biyu suka halarci wannan biki a wannan babban Otal. Dalilin kafa wannan qungiya shi ne don raya garin Kaduna da jin daxin jama'a. A wannan taro an zavi shugabannin qungiya kamar haka:

Mista D. I. Umodu a matsayin Shugaba, da Malam Bala Keffi, a mataimakin Shugaba, da Mista John Dike, Ma'aji, da Mista Ibiam Sakataren kuxi da Malam Aliyu Adama, Sakatare, da Mista O. Inyang, mataimakin Sakatare, da Mista

Sagay mataimakin Sakataren kuxi. An kuma zavi Laniran da Jalingo a matsayin "Auditor, " wato Mai Binciken kuxi.[1]

A wannan lokaci mutanen Kaduna suna da qarfi a harkokin Siyasa sosai, akwai manyan 'yan NEPU da NCNC a wannan gari. A shekarar 1953, Malam Bala Keffi a lokacin yana Sakataren reshen jam'iyyar NEPU a Kaduna, ya rubutawa Qaramar Hukuma wasiqa yana qorafi akan ayyukan Majalisar Gari wato Kaduna *Advisory Council*, yana kuma zarginta da gazawa wajen raya gari da inganta rayuwar da jin daxin al'ummar Kaduna. A dalilin da dagewar da 'yan Siyasa suka yi, a wajen neman inganta rayuwar mazauna Kaduna, ya tilasta gwamnatin jiha duba wannan al'amari da idon basira. An kafa kwamiti da zata duba harkokin birane a Arewa a ranar 3 ga Yunin shekarar 1953.[2]

A rahoton wannan kwamiti, gwamnati ta fito da shirin kula da Qananan Hukumomi da ke birane ta xaukar matakai guda uku: En'e ta kafa Majalisar gari, wato *Town Council* ta kuma bata ikon zartar da harkar kuxi, a maida Majalisar qarqashin En'e, wadda kuma ke da ikon akan kasafin kuxi da qiyasi waxanda za a sanya cikin kasafin En'e, da kuma shirya kasafin kuxi da qiyasi waxanda ke dabam da na hukuma.

A matsayin Kaduna kuwa na tushen mulki, "'yan Kwamiti sun ba da shawarwari da gwamnati ta karvi harkar mulkinta. " A dalilin shawarwarin da gwamnati ke samu, sai ta kafa Majalisar Gari, mai mambobi talatin da biyar, a qarqashin Magajin Gari Sambo, da mataima kansa da ake zavowa daga Majalisa. Wakilan wannan Majalisa ma, ana zavensu ne daga qabilu mazauna Kaduna, yawan wakilai na da dangantaka da yawan qabilu. Haka kuma Hukumar En,e na aiko da wakilanta guda huxu.[3] Duk waxannan matakan an xauke su ne saboda a inganta sha'anin mulki a Kaduna, a kuma anga an samar da zaman lafiya a tsakanin qabilu iri-iri da suke zaune a wannan gari, waxanda suka kuma bambanta a addini da al'adu.

A lokacin da batun kafa Kaduna Yankin Qasar Hedkwata wato Kaduna *Capital Territory* ya taso, sai da Leftanan Gwamna ya kafa kwamiti da zai shata iyakar wannan yankin Qasar hedkwata, a qarqashin Shugabancin Razdan na Zariya, wanda kuma ya qunshi Magajin Garin Sambo da Sarkin Kakuri da wakilai daga Majalisar gari, a matsayin mambobi.[5] Saboda kada a riqa rikice-rikice a kan iyakar wani yanki da yankin qasar Hedkwata. A dalilin haka ne zaman wannan Kwamiti na ran 4 ga Agustan shekarar 1954 suka ba da umarnin da a shigar da Kurmin Mashi da Kakuri cikin wannan yanki. Domin haka wannan yanki ya

---

1 Nigerian Citizen, 17 ga Satumba 1952, shafi na 3

2 E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na 454

3 NAK, Zaria N.A. 24/10/S.1: *Advisory Board Sabon Gari Kaduna and Zaria*.

qunshi Kawo, Tudun-Wada, Barnawa, Kakuri, Maqera,da Unguwar Rimi.[1] Kwamitin kuma ya amince da Kantoma ya karvi shugabancin "Kaduna Township " da yankunan da ke qarqashin En'e.

Mulkin Kaduna tun farko, kamar mulkin Nijeriya yake, rigar siliki ka rataye nan, can kuma ya sulluve. Saboda an sami matsaloli wajen tafiyar da mulkin gari, kamar yadda ake so, sai aka zartar da hukuncn maida yankin Hedkwatar Qasa, wato Kaduna *Capital Territory*. (KTC). Duk waxannan qungiyoyi da sauran irinsu sun ba da su taimakowajen kawo zaman lafiya da annashuwa a cikin garin Kaduna.

Qungiyar Samari

An kafa wata qungiya ta Samari da yam matan Arewa a Kaduna. An buxe reshen wannan qungiya a Tudun-Wada Kaduna. Wannan reshen qungiyar har ya sami mambobi da suka yi yawan mutane xari biyar da hamsin. Sakataren watsa Labarai na qungiyar ya bayyana cewa wannan qungiya babu ruwanta da siyasa. Manufar kafa qungiya shi ne don haxa kan samari da 'yanmatan Jihar Arewa domin su zama tsintsiya maxaurin ki xaya. Domin kuma a zaburar da matasa don su yi aikin ci gaban qasa, su kuma zama masu ladabi da biyayya.

A lokacin da aka kafa reshen wannan qungiyar a Tudun-Wada Kaduna, an yi zaven shugabanni waxanda za su riqe alhakkin qungiya, har tsawon shekarar guda, kafin a sake zave. An zavi M. Balarabe Sa'idu ya zama Shugaba; M. Adamu G. Yunusa, Mataimakin Shugaba; M. A.L Shehu, Sakatare; M. Hassan Galadima mataimakin Sakatare. An kuma zavi M. Yakubu Yunusa a matsayin Sakataren kuxi, da M. Abdu Biu a matsayin Ma'ajin qungiya. M. Saidu Isa, shi aka zava mai Binciken Kuxi. Sakataren wassanni shi ne M. Sani Kwaleji da sakataren watsa Labarai Adamu G. Yunusa.

Har ila yau an zavi Shugaban mata Madam Lami Katsina da Madam Ateze Tiv, a matsayin mataimakiyar Shugaba; sakataren sashen mata shi ne M. Haliru. Haka kuma reshen ya kafa kwamiti wanda zai riqa kula da al'amuran qungiyar. An kuma kafa waxannan kwamiti, kowane kuma yanada 'yan kwamiti masu yawan mutane bakwai zuwa yoma sha huxu. Akwai kwamitin ilimi qarqashin shugabanci M. Adamu G. Yunusa; da kwamitin kuxi qarkarshin shugabancin M. Yakubu Yunusa. Haka kuma M. Adamu G. Yunusa, shi ne zai jagoranci kwamitin watsa labarai. Kwamitin wasanni kuwa na qarqashin M. Usman Bobo da sauransu.

Waxannan kwamitoci sun yi ayyukan ci gaban reshen wannan qungiya, An kuma yaba masu. Alal misali, a lokacin taron bikin zaman Nijeriya Jamhuriya a

[1] NAK, Zar Prof/1954: *Administration of Kaduna Townshishafi na*

Kaduna, reshen wannan qungiya ne ya yi masu wani wasan kwaikwayo, wanda ya qayatar sosai har ma muhimman mutane da suka halarci wannan taro suka yaba wa qungiyar. Yana daga cikin manufofin wannan qungiya yin wasanni masu ilmantarwa da qayatarwa, waxanda kuma ake sa ran za a riqa nuna wa a sinima.[1]

[1] GTK 6 Disamba 1963, shafi na 14

KASHI NA TAKWAS

Kafuwar Unguwanni

Dalilin Kafa Unguwanni

Cizon qudan tsando shi ke haddasa ciwon bacci da makanta. Akwai waxannan qudaje da yawa a dajin doka musamman a gavar kogi. Saboda haka mazauna wannan yanki na cikin haxarin kamuwa da waxannan cutuka. Dalilin haka ya sa Turawan mulki suka xauki matakan kare kansu da jama'ar gari daga xaukar waxannan cutuka. An ce rigafi ya fi magani. Sassare itatuwa da ciyayi waxanda su ne wuraren hayayyafar waxannan qudaje, yana taimakawa wajen rage su. Saboda haka sai aka ga Turawan da ke zaune a *European Reservation Area* da 'yan qasa da baqi da suke zaune a Sabon Gari Doka suna cikin haxarin kamuwa da cizon qudan tsando wanda ke haifar da ciwon barci. Domin suna cikin tsakiyar daji ne. Ana fama da matsalar qudan tsando, sai matsalar karancin abinci ya hudo kai.

A shekarar 1926 Leftanan Gwamna H.F. Palmer saboda yawan qorafin da ake samu musamman akan qarancin abinci ya ce: "Matsala ta biyu ita ce maganar abinci wadda take buqatar xaukar mataki cikin gaggawa. Duk da haka sai fa an samu hanyoyin da za a bi domin janyo hankalin jama'a da yawa da za su baro garuruwansu, su zo su kafa unguwanni su zauna a wannan waje. "[1]

Akwai matsaloli masu yawa da suka addabi jama'a da Turawa, musamman a qarshen yaqin duniya na farko. Bayan wannan yaqi ne sai aka sami qaruwar jama'ar gari cikin hanzari. Alal misali, yawan jama'a a shekarar 1918 dubu biyar (5,000) ne, amma a shekarar 1926 ya wuce dubu goma sha-biyu (12,000). Kwararowar jama'a zuwa wannan gari musamman baqi 'yan Kudu, ya tayarwa da Turawan Mulki hankali, saboda sun hango cewa ba da daxewa ba, garin zai cika da waxannan baqi. Saboda haka sai aka xauki matakin jawo 'yan Arewa zuwa wannan sabuwar hedkwata. Dalilin haka ya sa a farkon shekarar 1920 aka xauki shirin jawo 'yan Arewa zuwa Kaduna.

Har-ila-yau, akwai kuma wasu dalilai da suka sa aka xauki wannan shiri. Na farko, a bisa tsarin zama a Kaduna dokar gari tayi hani da zama a Sabon Gari ga wanda ba Badungure ba. Zaman Kaduna Township kuma sai Turawa, da Ma'aikata da Sojoji. Wannan ya sa garin ya zama kamar faqo saboda rashin jama'a. Ko da yake haka aka tsara, amma sai aka lura ana samun yawan hayayyafar quxan tsando a dajin doka saboda makeken dajin da ya kewaye garin

---

[1] NAK, SNP 15 ACC. 249 (1926); *Political Memo by H.E. Lt. Governor: Problems Confronting Nigeria.*

kamar kwabo a cikin babban aljihu. Dalili na biyu, shi ne a qarshen yaqin duniya na farko, an sami damar ci gaba da wasu ayyuka musamman aikin hanyar jirgi ta *Eastern Railway Projects* wanda aka ci gaba da ita a shekarar 1922, ya qara janyo kwararowar leburori zuwa Kaduna. A lokacin wannan aiki, akwai leburori dubu uku da xari biyar (3,500) waxanda suka zo daga lardin Zazzau. An kuma samu yawan mazaje kusan dubu huxu (4,000) a shekara waxanda suka zo wajen wannan aiki.[1]

Daga qarshe sai qarin yawan jama'a, ya haifar da qarancin abinci abin da ya tayarwa da gwamnati hankali. Alal misali, a farkon shekarar 1921 an ba da rahoton cewa abinci ya yi qaranci sosai har ma sai da muqaddashin Leftanan Gwamna ya riqa sayo hatsi daga garin Minna domin a sayar wa jama'a.[2]

Saboda waxannan dalilai sai aka lura cewa qarin samun jama'a zuwa Kaduna zai taimaka wajen yaqi da qudan tsando ta hanyar sare dazuzzuka wajen kafa unguwanni. Haka kuma jama'a mazauna waxannan unguwanni za su taimaka wajen noma abinci tare da bunqasa kasuwanci.

A farkon shekarar 1920 sai aka lura da irin wannan haxari da mazauna garin Kaduna ke ciki. Saboda haka aka xauki matakan maganinsu. Kafa unuguwanni a wuraren da suke da ba su wuce nisan kilomita goma daga Kaduna ba, yana xaya daga cikin matakin yaqi da qudan tsando. A duk wuraren da za a kafa waxannan unguwanni zai tilasta sassare itatuwa da ciyayi wanda zai kore waxannan muggan qwari musamman sauro da qudan tsando. Saboda haka sai aka xauki shirin kewaye garin Kaduna da unguwanni domin su zama kamar shinge ko garkuwar kare garin daga waxannan qwari.

A farkon zuwan Turawa Kaduna ba sa son zaman jama'a kusa da su domin sun ce suna tsoron xaukar ciwo da yawan sace-sace. Ayya, amma sai aka fahimci ai jama'a rahama ce. Domin haka ne sai aka sauya dokar neman jama'a ta maye gurbin korar jama'a daga Kaduna. An tashi haiqan wajen sassare itatuwan doka a wuraren da aka kira *Tse-tse Area*, wato mazaunin qudan tsando. A cikin wannan sabon shirin ne Turawan Mulki suka nemi taimakon Sarakunan Arewa domin su taimakesu, su turo jama'a su zo su kafa unguwanni a Kaduna. Turawan kuma basa son a cika waxannan unguwanni da jama'a daga wasu wuraren da ba 'yan Arewa ba. Saboda suna ganin yin hakan zai vatawa Sarakuna rai abin da suke gudun gani. Don kuwa Sarakunan sun gargaxi Turawa da kada su cika wannan hedkwata da 'yan Kudu. Wannan ya nuna kishin Sarakuna ne, ya maida Kaduna garin 'yan Arewa. In ba haka ba da tun farko 'yan Kudu sun mallaketa.

A wannan shirin kafa Unguwanni ne, aka kafa doka da ta xaukewa mazauna waxannan unguwanni harajin shekara biyar. Abin da ake so shi ne a kafa

---

[1] NAK, SNP 9 100/1924: *Zaria Annual Report for 1923*.

[2] *Ibid*., 9 697/1927: *Kaduna Township Annual Report*, 1921.

unguwanni cike da jama'a maqil. Dalilin haka ne aka kafa Tudun-Wada. Sarkin Kano Abdullahi Bayero ya turo jama'a suka kafa unguwar Kanawa, da haka kuma aka kafa unguwar Munci, inda wasu jama'a daga qabilar Tiv guda xari uku da suka taho daga yankinsu. Waxannan unguwanni banda Tudun-Wada har ba su tallafi aka riqa yi saboda zuwansu sabon waje kafin su zama 'yan gari su sami sana'ar yi. Alal misali, daga watan Afrilu zuwa watan Nuwambar shekarar 1929, mutanen Unguwar Kanawa sun sami tallafin kuxi har fam xari biyu da hamsin daga asusun binciken kuxan tsando wato *Tse-tse fly investigation*.[1]

Jama'ar da aka janyo zuwa Kaduna daga sassan Arewa talakawa ne, waxanda dokar gari *Township Ordinance of 1917* ba ta ba su damar zama a Kaduna ba, amma sun kafa Unguwanni da suka dace da su. Ko da yake Turawan Mulki ne suka kawo wannan shiri da ya dace da cimma bunkatunsa, amma 'yan Kudu sun yi wa wannan shiri rina. Jaridunsu kuma sun soki wannan lamiri da kakkausan harshe. 'Yan Kudu sun soki kafa gari a wajen da babu kowa, da kuma xaukar matakan da za su fifita Arewa fiye da kudancin Nijeriya. Har ma rubuta wasiqar su kan wannan tsari suka yi, a wani shaguve da cewa "wani waje a Nijeriya, " wanda aka buga a mujallar *African World*. A wannan wasiqa, 'yan Kudu sun yi kakkausan suka ga gwamnatin Lugga, inda suka zarge shi da girman kai, suka yi masa nuni da gazawar wannan shiri nasa. Suka yi masa misali da rashin bunqasar garin Kaduna da Port Harcourt.[2] 'Yan Kudu, mutane ne masu sonkansu, da kishin jihohinsu, sun kuma yi qaurin suna wajen butulci. Hasali ma dai, duk shirin da ba zai amfane su kai tsaye ba, zai sha suka da tokari.

Waxannan soke-soke sun yi wa gwamnatin Lugga qaimi saboda ta himmatu wajen gyaran tsarin kafa Unguwanni. Saboda haka ne ma ta xaukewa mazauna waxannan Unguwanni harajin shekara biyar. Dalilin haka ya sa aka samu zuwan jama'a daga sassa daban-daban daga Arewa waxanda suka kafa Unguwanni. A shekarar 1926, an samu qarin mutane xari takwas da tamani da takwas (488); xari da talatin da biyar (135) a 1927; xari da arba'in da tara (149) a shekarar 1929. A cikin wannan qarin jama'a da aka samu ne sai mutane xari biyar da hamsin da huxu (554) suka sauka a garin Maqera.[3]

A hankali sai jama'a ke kwararowa suna zama a Unguwanni, har ma wasu jama'a da ke zaune a Sabon Gari sun yi qaura zuwa waxannan Unguwanni saboda neman sauqin 'zaman tare da walawa'. Sannan kuma ga rashin biyan haraji har na tsawon shekara biyar. Alal misali, a tsakanin shekarar 1926 zuwa 1927 an qiyasce magidanta xari biyar da talatin da takwas (638), waxanda suka qunshi maza xari

---

1 Annual Report for 1929: *Kaduna Township*

2 *African World*, London, April 26, 1919.

3 NAK, SNP 17/1-1237: *Encouragement of Settlements within 10 miles radius of Kaduna*.

biyu da casa'in da bakwai (297) da mata xari biyu da arba'in da xaya (241) sun taso daga Sabon Gari sun kuma tare a Tudun-Wada. Akasarin waxannan magidanta masu sana'ar hannu ne.[1] Wata qila sana'arsu za ta fi saurin bunqasa a wannan Unguwa.

Haka kuma wasu manoma qabilar Tiv wato Munci sun taho zuwa Kaduna, sai suka kafa wata unguwa da ke Arewa maso Gabashin Maqabartar Turawa. Wannan unguwa ta haxa har da gavar kogin Kaduna inda waxannan manomasuka shiga noma shinkafa.[2] A hankali sai Unguwar Munci ta fara girma har a watan Nuwamban shekarar 1929 aka qara samun qarin mutane arba'in da uku (43).

An ce Kanawa ne suka zo da noman shinkafa a Kaduna a shekarar 1920.[3] A watan Afrilu na shekarar 1929 an qara samun qarin zuwan Kanawa saba'in da biyu daga Kano, sun qara bunqasa Unguwar Kanawa. Wasu Sakkwatawa sun zo sun kafa Unguwar Waziri, yawan mazauna a wannan unguwa sun kai sittin da huxu (64) a shekarar 1929.[4] A kusa da wannan Unguwa ne tsohon Sarkin Madagali Muhammadu yaji ya kafa wata Unguwa.

Akwai unguwanni masu a yawa da aka kafa a sassa da dama a kewayen Kaduna, kowace unguwa na da shugaba, wanda ke taimakawa jama'ar Unguwar wajen kai koke-kokensu ga hukuma, ko raba filoti ko sha'anin aiki da kasuwanci. Akwai wasu Unguwanni da ba su wuce nisan kilomita biyar da Kaduna ba kamar Unguwar Ebunu, da 'yan Renci, da 'yan Keke da Jatau Helma da Abdu Helma da Kwangila. Dukkansu sun jawo jama'a a sassa daban-daban na wannan gari. Haqiqa, tsarin jawo jama'a zuwa Kaduna don kafa unguwanni ya cimma nasara sosai. Saboda haka waxannan unguwanni da bunqasar jama'a sun taimaka wajen yaqi da qudan tsando wanda shi ne maqasudin kafa su jama'a kuma sun bunqasa garin.

Saboda sassaucin da jama'a ke samu a waxannan unguwanni, sai jama'a ke qara kwararowa kafin xan qaramin lokaci har unguwanin sun bunqasa sosai, har ma yawan jama'a a shekarar 1929 a Sabon Garin Doka sun kai dubu bakwai (7000). A wannan shekarar, yawan mutane a Kaduna sun kai dubu goma da 'yan kai. Ga kasafin yawan jama'a a Kaduna Township a shekarar 1929:

---

1 NAK, SNP 17/1-1237: *Encouragement of Settlements within 10 miles radius of Kaduna*

2 *Ibid*. 17/1-11617: *Kaduna Township Annual Report*; 1929

3 *Ibid*.

4 *Ibid*. 17/2/-1237

Layin 'yan Sanda	338
Layin Sojojin WAFF	761
Layin 'yan Gadirin	179
Layin Asibitin Jama'a	209
Unguwar Akawuna	493
Unguwar Turawa (da ma'aikatansu)	898
Kaduna Junction	713
Firizin	188
Sabon Gari	7082
Jimilla	10,861[1]

Koda yawan jama'a a Kaduna Township ya kai wajen dubu goma sha-xaya, yawan jama'a a unguwanni kuwa ya tasamma dubu uku a shekarar 1929. Yawan mutane da kewaye ya kusan kai dubu goma sha-huxu (14,000). Saboda haka sai *Station Magestrate* ya rubuto cewa:

Leftanan Gwamna ya umarceni da in faxa maka Mai martaba, ya lura yawan jama'a a Kaduna Township, ya ninka a cikin shekaru huxu, kamar yadda qididdigar shekarar 1924-1928 ta nuna. Wato yawan mutane da ke cikin Kaduna Township da kewayen da ke da nisan mil biyar ya kai yawan mutane dubu goma sha-huxu."[2]

A shekarar 1929, kasafin jama'a a unguwanni da ke Kaduna sun kai kamar haka:

Unguwar Sarkin Noma	29
Unguwar Munci	187
Unguwar Waziri	72
Unguwar 'yan Keke	26
Unguwar Jatau Heluma	30
Unguwar Kwangila	188
Unguwar Abdu Heluma	65
Unguwar 'yan Fenci	38
Unguwar Ebanu	49
Kawo	339
Tudun-Wada	700
Barnawa	130
Maqera	540

---

1 A.K Medugbo, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 110

2 *Ibid*. shafi na 111

Kurmin Kakuri	487
Kurmin Mashi	89
Kudenda	103
Jimilla	3,072[1]

Tsarin kafa unguwanni a Kaduna ya cimma nasara saboda jama'a qabilu daban-daban sun kwararo zuwa Kaduna. A shekarar 1931 an samu bunqasar waxannan unguwanni da jama'a da qabilu daga kusan kowane yanki na Nijeriya, amma 'yan Arewa sun fi yawa. Wannan tsari ya gamsar da Turawan Mulki, ya nuna kishin da Sarakunan Arewa suka nuna na taimakawa wajen maida Kaduna garin 'yan Arewa. Wannan ya yi tasiri sosai a zamantakewar jama'ar mutanen wannan gari a wannan zamani.

Tun asali, an shirya zaman qabilu ya dace da addini da al'adunsu, an bi qwaqqwafin wannan shiri wajen kafa unguwanni. Zama a Kaduna Township sai Turawa, da Akawuna, da Ma'aikata, da Sojoji da 'yan Sanda tare da Dungurawa. Saboda haka zaman Kaduna Township sai ya zama na haxin gambiza. Amma akasarin mazauna Tudun-Wada da Maqera da Kakuri da Kawo Hausawa ne. A kuma unguwannin da Musulmi suka fi yawa ba a ba da izinin sayar da giya.[2] Saboda qoqarin da mazauna wajen ke yi na aiwatar da shari'ar musulunci dai-dai gwargwado. A wasu unguwannin kuwa sharholiya ake yi dare da rana.

A duk inda jama'a suka taru, suka kafa unguwanni su kan naxa shugabanninsu, da qungiyoyi iri-iri domin samun zaman lafiya da ci gaba. Akwai qabilu iri-iri a kowace unguwa, saboda haka ne hukuma ta amince da waxannan shugabanni. Kamar Sarkin Hausawa da Sarkin Yarbawa da Sarkin Ibo da sauransu. Ta su ne jama'a ke kai koke-kokensu ga hukuma, domin haka ne garin Kaduna ya daxe da zaman lafiya da lumana a tsakanin mazauna garin.

Ko da yake Kaduna ta yi suna wajen nuna wayewa da 'yan garanci da sharholiya tare da rashin girmama na gaba, amma akwai unguwannin da suka daxe suna qoqarin riqe al'adu da dattaku. A matsayin Kaduna na bariki ya kawo halayyar barikanci saboda tasirin Sojoji da 'yan Sanda a wannan gari. Hulxa da ta'ammali a tsakanin qabilu ya gurvata al'adunsu, ya kuma assasa barikanci a kansu. Irin wannan zama na bariki ke yawaita aikata laifuka da watsi da al'adu da sakaci da addini. Waxannan matsaloli ne da suke addabar birane musamman a garuruwan da Turawa suka kafa. Garin Kaduna ya yi suna wajen tavarvArewar al'adu musamman a qarshen yaqin duniya na biyu, lokacin da sojoji suka dawo daga yaqi.

---

[1] A.K Medigbo, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 111

[2] *Ibid*. shafi na 156

A wannan gari hukumar tsaro da shari'a ta xau tsauraran matakai, wajen ganin jama'a na bin doka domin samun zaman lafiya da lumana. A shekarar 1930 aka sanya kowane shugaban qabila ya zama wakili na Kotun Gargajiya da na Alqalai. Ko da yake an lura qabilu musamman 'yan Kudu sun fi zuwa Kotun Majistare wajen kai koke-kokensu, saboda sun fi ganin wannan kotun za ta fi masu adalci. Duk da haka hukuma ta tabbatar da zaman lafiya a Kaduna. gwamnati ta ba da shaidar haka a rahotonta na shekarar 1931 kamar haka: "A Kaduna Township Kotun Gargajiya ta qunshi wakilan qabilun al'ummomin lardunan Arewa da kewaye. Kotun ta tafiyar da aikinta cikin lumana tun kafuwarta a shekarar 1931, ta kuma gamsar da kusan dukkan sashen al'ummomi. 'yan Sanda ke kula da harkokin jama'a a cikin Kaduna. Saboda haka ne Kotun Gargajiya ba ta samu qararrakin laifuka ba. "[1]

Unguwar Lebura

Saboda yawan leburorin da ake samu a kullum a cikin Sabon-Gari, sai aka kafa masu unguwa a Yamma da kasuwa (wajen tsohuwar kasuwar Fanteka a yanzu). Ita wannan unguwar aka sa mata suna Unguwar Leburori kafin qarshen shekarar 1920. Akwai xaruruwan leburori a wannan unguwa jingim. Unguwar lebura ba ta qarqashin hukuncin *Station Magestrate* saboda tana cikin qasar Zariya ce, dalilin haka sai aka tattauna da Razdan na Zariya bisa yadda mazauna wannan unguwar hukuma za ta san da zamansu. Saboda wannan dalili sai lyan Gari, Iya Abdullahi ya naxa shugaba, wato mai unguwa wanda zai kula da shugabancin waxannan jama'a. Wanda aka naxa shi ne Jakadan Sarkin Kawo Abdullahi mai suna Kwasau.

Iya Abdullahi Malami ne wanda ya yi amfani da basirarsa wajen tafiyar da harkokin jama'a. A Kinkinau ne tushen mulkinsa yake, inda ikon mulkinsa ya haxa da Unguwar Lebura, da sauran qauyukan da ke gewaye da kuma Arewa da kogin Kaduna. Ya sami muqamin Iya a tafiyad da 1903 ya kuma yi ritaya a shekarar 1931.

A hankali wannan unguwar sai cika take yi da jama'a kuma Sarkin Unguwar Leburori Kwasau yana kuma qoqarin tafiyar da shugabanci sosai don tabbatar da zaman lafiya da lumana. Abin ka da garin leburori da gari ya waye in rana ta fito sai ka ji garin ya yi tsit ba ka jin xuriyar kowa daga yara sai mata. Amma da zarar Yamma ta yi leburori sun dawo wajen aiki sai unguwar ta cika maqil da jama'a.

Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim Xan Sarkin Kawo Abdullahi, yana xan shekara goma sha-shida, a lokacin da wannan Tsangayar Leburori aka naxa mata shugaba, a kuma idonsa ne ya ga bunqasar wannan Unguwar har a lokacin da aka

[1] A.K Medigbo, *Kaduna, Nigeria*, shafi na 160

haxa ta da Kinkinau inda suka zame Tudun-Wada. Ga abin da ya ce: "Asalin wannan Unguwar Lebura a wajen Panteka ta yanzu aka kafata. Da ta zama a qarqashin Iya Abdullahi sai ya yi mata Sarkin Yalwa. Wanda aka yi wa wannan sarauta kuwa shi ne Kwasau. A lokacin da Kwasau ya samu sarauta yana riqe da muqamin Jakadan Sarkin Kawo Abdullahi. Amma duk da wannan naxi na sa na Sarkin Yalwa, jama'a sai suka ci gaba da kiranta Unguwar Lebura ba Unguwar Yalwa ba kamar yadda Iyan ya so. "[1]

Shirin Kafa Tudun-Wada

Tsarin zama a garin Kaduna yana da nasaba da bambancin launin fata da bambancin muqami da na addini. Waxannan bambance-bambancen sai suka fito fili sosai musamman a lokacin Gwamna Clifford wanda ya gaji Lugga. Tun a shekarar 1919 wannan Gwamna ya yi iqirarin shimfixa waxannan bambance-bambancen a zamantakewar mutane a Kaduna. Kwararowar jama'a daga sassan Arewa, musamman daga Kano da Zariya zuwa Kaduna sun sosawa Turawan mulki rai. Alal misali, Unguwar Lebura da bunqasarta sun yi wa masu mulki qaimi wajen xaukar matakin ganin an kawar da wannan Unguwa, an kuma hana bunqasar Sabon Gari don gudun cinKwason jama'a, wanda suka ce ka iya kawo varkewar ciwo da sace-sace.

Saboda a keve unguwar Turawa daga sabon garin doka ya sa aka bar wani babban kwazazzaban da ke tsakanin waxannan unguwanni domin su qara faxin wajen da ba a son jama'a su zauna wato *Non-Residential Area*. Haka kuma duk inda aka samu yawan jama'a sai a tsoraci za su kawo cinKwaso wanda ka iya haifar da matsololin da rahoton Gwamna ya bayar wajen tabbatar da bambancin unguwanni a garin Kaduna. Amma ba a xauka yin haka nuna bambamcin launin fata ba ne; matakan kula da rigafin xauka da yaxuwar cutuka ne suka tilasta yin haka. Saboda haka sai taruwar jama'a a unguwar Lebura ta zama wata barazana ga Turawa domin haka sai suka xauki matakan maganinta da gaggawa.

A wani rahoto da Gwamna Lugga ya bayar wajen ba da hanzari a kan tsarin bambancin launin fata a zaman garin Kaduna ya ce: "Dalilin da ya sa aka shata babbar fili ba na mahalli ba, "non-residential area " shi ne domin a keve Turawa daga cizon sauro. Saboda im ba a kevesu ba sauro na iya xaukar ciwon zazzavi ko ciwon shawara, *Yellow Fever* daga 'yan qasa wato "Natives " ya sa masu waxannan cutuka... Wannan shinge kuma zai kare Turawa daga varkewar gobara da hargitsi da yawan kaxe-kaxe da zai dami Turawa idan suna zaune a mahalli da ke kusa da jama'a. "[2]

---

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu ran 15 ga Disamba 1984.

[2] NAK/MPC/427; *Extra*: *Headman for Kaduna Townshishafi na*

Jama'a Rahama ce. Koda Turawa ke qyamar kusantar jama'a saboda wasu dalilai da suka ba muhimmaci, amma sai gashi sun zo daga baya suna neman jama'a da su zo Kaduna su kafa unguwanni a sassa daban-daban. Saboda barin makeken fili a dajin doka na taimakawa wajen hayayyafar qudan tsando wanda ke haifar da ciwon bacci da makanta. Dalilin haka ya sa su xaukar babban matakin yaqi da qwari da sauran muggan halittu da ke kawo barazana ga lafiyar jama'a a wannan gari. Wannan ya tilasta yaqi da qudan tsando ta hanyar, ba da tallafi ga jama'a domin su kafa unguwannin da za su yi wa unguwar Turawa wani shinge daga addabar qwari da qudan tsando.

An kafa 'yan kwamiti waxanda aka ba alhakkin shawo kan wannan matsala da ke damun Turawan mulki. Sai 'yan kwamitin Lardin Arewa na tsarin garuruwa wato *Northern Province Town Planning Committee*, suka fara zamansu a ran 25 ga Nuwamban shekarar 1924. A wannan zamanne wani wanda aka kira Shugaban Garin Kaduna wato *Headman for Kaduna Township*, ya rubutawa Hukuma da ra'ayinsa a ran 17 ga Yunin shekarar 1924 kamar haka: "Ina jin wannan batu na matsayin mutanen gari, ya kamata a yi nazarinsa, don a maida jama'ar Unguwar Lebura qarqashin mulkin En'e ta Zariya. A yanzu garin na bunqasa da jama'a, ba ma son mu bar tarin jama'ar da ba sa qarqashin En'e.[1]

Ko da yake wannan "Headman, " bai rubuta sunansa ba amma ya nuna alqiblar Kwamitinsa wanda yake shi ne maida jama'ar Tsangayar leburori qarqashin ikon En'e. Amma ba maida jama'a qarqashin En'e kawai maganar ta tsaya ba, a'a, sai an samowa baqi wajen zama nesa da Kaduna. Saboda haka sai Keftin E.H.B Laing ya rubuto wa Sakataren Larduna waxannan shawarwari inda ya ce:

> *Sakatare,*
>
> *Wata qila hanya mafi dacewa da za a bi ita ce, a kafa gari a qarqashin Hakimin Kangiwa (Iyan Gari) domin a yanje hankalin masu son zaunawa a Sabon Garin Doka wato Non-European Reservation.*
>
> *Za a samu wuri da ya dace a Arewa-maso Yammacin Fidaburdi ko Tsangayar Leburori wati Labourer's Camp ko kuma Kudu da buzaye (wajen koyan harbi) wato Musketry Range.*
>
> *Wa su jama'ar da ke zaune a Sabon Gari a yanzu, a iya janyo hankulansu da su tashi su koma wannan waje, idan za a biya su wata yar diyya. Kafa sabuwar kasuwa ka iya jan hankulansu zuwa can, wani abu da zai amfani jama'ar Kaduna.*

---

[1] F.D Lugard, *Political Memoranda: Revision of Instructions to Political Officers*, London (1918) shafi na 420

Ni ban amince da waxannan mutane da su zauna a qarqashin mulkin masarautar Sarakuna Musulmi ba wato "Muhammedan Emirate, zan fi so inga duk waxannan sabbin unguwanni sun koma qarshin En'e, a bar cikin garin Kaduna ga Turawa da 'yan Afirka waxanda ala'adunsu ya kai wata daraja abar lura. Don haka ba zan so inga ana kafa gidaje waxanda ba su dace da tsari mai kyau da kuma tsabta ba.

Wani abu da ya zama gamo da katar a wannan lokaci shi ne su ma 'yan Sabon Gari sun fi so a maida su qarqashin En'e, wannan buri na fitowa fili musamman ga rukunin jama'a da ke gidaje a Tudun-Wada Zariya.

Daga qarshe zan ce abu ne mawuyaci a zartar da tagwayen iko akan jama'ar wannan waje ina kuma jin ba zai yiwu ba.

Sa hannu E.H.B. Laing (26.6.24)

Keftin Laing ya riqe muqamin Razdan ya daxe yana cikin sha'anin mulki, amma ba shi da sassaucin ra'ayi wajen nuna bambancin launin fata da kambama al'adun Turawa. Yana son tsarin zama da ya dace da al'adu irin na Turawa. Kusan ra'ayinsu xaya da Gwamna H. Clifford. Abin da yake nufi da tagwayen iko kuwa, shi ne mulkin *Station Magestrate* da na En'e akan mutanen unguwar lebura, a wajensa akwai bambanci. Amma shi Laing yana nufin da ikon Razdanne ta mulkin En'e ba takan Sarakuna ba. Haka kuma Sakataren ya sami qarin shawarwari daga mista Allan wanda yake shi ne babban jami'in Tsabta *Senior Sanitary Officer* (S.S.O) kamar haka: Da Sakatare G.S Browne ya sami wannan wasiqa ta sa sai ya aikawa Razdan na Zariya da wannan saqon cikin hanzari:a ran 17 ga Junin shekarar 1924. "Ina mai farin ciki in za ka bani na ka shawarwarin akan batun da aka aiko a sama. "

Wani abin lura shi ne Turawa suna bin al'amura cikin natsuwa tare da aiki da da hankali. Ga su kuma da hangen nesa. A wannan lokaci jama'ar Tsangayar Leburori ba su san abin da Turawan mulki ke shirin yi ba. Abu ne mafi sauqi a tarwatsa 'yan wannan tsangaya ko kuma a yi masu xiban karan mahaukaciya a kai su daji a zubar. Amma ba a yi haka ba, saboda gudun zalunci. Abin da aka yi, sai aka kafa kwamiti na musamman wanda yake da alhakkin samo makomar 'yan 'Labourers Camp'. Da akwai wani gari a dajin Doka, da haka za a yi masa kafin a gina Kaduna. Amma sai yanzu ake qorafin wai Turawa sun tarwatsa wata qabila cikin daji, wanda ko kaxan bai faru ba. Inda za a maida jama'a ma sai da aka tura masana yanayi suka binciki wajen ko zai dace da gina mahallin jama'a. Wannan shi ne adalci.

Idan kuma aka duba wajen zamantakewar jama'a, nan za a ga wallan Turawa saboda qyamar zama da 'yan qasa a waje xaya komai iliminsu da kuma nisantar

sauran jama'a saboda wai su na tsoron dauqar ciwace-ciwace da gudun sace sace daga Jama'ar gari. Haka kuma ba su cika son hayaniyar jama'a sosai ba. Waxannan dalilai da makamantansu sun taimaka wajen tsara zama mai nuna bambanci launin fata da matsayi a garin Kaduna. Amma baza a zargesu da yin haba saboda da waxannan halaye ne suka kevantas da 'yan qasa. Haka kuma ba a raba su da aqidar jari-hujja wadda ke da tasiri a halayen su da zamanta kewarsu da sauran al'ummomi.

Kafa Tudun-Wada

Sabon garin Doka sai qara bunqasa yake yi a kullum, saboda jama'ar da ke kwararowa daga ko'ina a Nijeriya suna neman mahalli. Amma duk da unguwar leburori da aka kafa jama'a sai bankowa suke yi ta ko'ina, suna neman waje don su gina gidaje a cikin Sabon Gari. Ganin wannan abu fa, sai Turawa suka tashi neman kafa wani gari nesa da Sabon Gari a cikin shekarar 1924.

Domin gudun kada a bar jama'a su bunqasa Sabon Gari ba tare da suna qarqashin hukuma ba, da kuma buqatar Turawa na son a bar garin Kaduna ga Turawa, 'yan Sabon Gari da waxanda suke sun xauki xabi'u irin na Turawa. Sai maganar kafa Tudun-Wada ta taso gadan-gadan. Idan su ma 'yan Sabon Garin na son zuwa garin, to, ana iya ba su kuxi don su tashi su tafi garin da za a kafa. A wancan zamani ganin yawan jama'a xaruruwa masu son filaye a cikin Sabon Gari ya tayar da hankalin Turawa, saboda haka sai aka kira taron masu tsarin gari *Town Planning Committee* domin su tattauna wannan matsala su kuma ba da shawarwari hanyar da za a bi don a shawo kan wannan abu.

'Yan wannan kwamiti sun yi zaman su don tattauna wannan matsala a ranar 25 ga watan Nuwamban shekarar 1924, a qarqashin shugabancin Mista G.S. Browne. Maqasudin wannan taro kuwa, shi ne a nemo hanyoyin da za a bi don janye hankulan jama'a daga son zaman Sabon Garin Doka.

A lokacin wannan taro na 'yan kwamitin tsarin gari, sun zartar da a kafa wani gari sabo nesa da garin Doka qarqashin Iyan Gari da ke Kangiwa, kuma a cire wa mazauna wannan sabon wuri haraji har na tsawon shekaru biyar. Muddin aka yi wannan abu in ji 'yan kwamiti, to, xaruruwan jama'ar nan hankulansu za su koma ga wannan sabon wuri, idan kuwa haka ta samu to, Sabon Garin Doka ya kuvuta daga cinKwason jama'a ke nan. An tashi wannan taro da qudurin kafa sabon muhalli da kuma cire wa jama'ar wajen harajin shekara biyar.

Wajen zavar filin da ya dace da a kafa wannan sabon gari kuwa, sai Razdan Mista E.H. Laing ya bayar da shawara da a kafa wannan gari mai tsari irin na Tudun-Wadan Zariya a qarqashin garin Kangiwa, inda kuma zai dace da kafa wannan gari kuwa wurare uku ne: (1) Kudu maso Yammacin fidaburdi (ii) Arewa maso Yammacin unguwar leburori, da (iii) kudancin buzaye.

Babban Jami'i mai kula da tsabtar gari, "Senior Sanitary Officer " Mista W. Allan shi ya dubo waxannan wurare, shi ne ya kuma zavi kudancin Buzaye wato "musketry range " inda ya ce akwai qasar noma kusa da wannan wuri. Ya kuma amince da aka kafa Tudun-Wada a wannan wuri.

gwamnan wannan lokaci Mista H. Clifford ya tara qananan Sarakunan garuruwan wannan wuri, domin ya bayyana masu wannan shirin da ke tafe. gwamnan ya ce da su, za a tashi jama'ar Unguwar Leburori daga inda suke, kuma za a kafa gari mai suna Tudun-Wada saboda za a yi gidan Gwamna a Badiko ba a kuma son hayaniyar jama'a ta dame shi.

Gwamna Clifford ya tara waxannan Sarakuna ne a wani daji, da ke Kudu da Buzaye wato inda za a kafa Tudun-Wada. Su waxanda aka yi taron da su kuwa su ne: lya Abdullahi da Sarkin Kawo Abdullahi. Gwamna ya ce da su a wannan wajen za a yi safiyon fulotai don mutanen Kangiwa (inda Alqali yake), za a tayar da su a ba su fulotai a wannan wuri haka kuma za a gina babban xakin shari'a da gidan Alqali. Haka kuma mutanen unguwar lebura su ma za a dawo da su nan a ba su fuloti.

Gwamna Clifford ya ce da lyan Gari Abdullahi, "Mun qara ma girma don haka za ka koma gidan Magaji Sambo da ke Maqera shi kuma Magaji Sambo ya koma Cikun. Babban baturen ya bayyana cewa, "Mun yi wa Wanya da ke Kujama ritaya. Kujama da ke qarqashinsa mun qara wa Magaji Sambo da ita. " An kuma yi wa Magaji Sambo Tabari qarin girma a wannan lokacin da ake shirye-shiryen kafa Tudun-Wada. "[1]

Haka ko aka yi mutanen Kangiwa da na Unguwar Leburori duk suka taso aka bai wa kowa fuloti, sannan aka yi babbar kotun shari'a da gidan Alqali kamar yadda Gwamna Clifford ya bayar da umarni, cikin hanzari wannan unguwa sai ta cika maqil da jama'a. Ko da yake tun farko an sa wa wannan gari Tudun-Wada, amma sai jama'a suka ci gaba da kiran wurin Unguwar Leburori. Sarkin Unguwar Lebura Kwasau sai ya zama Sarkin Tudun-Wada na farko. Tsarin wannan gari an yi shi ne kamar na Tudun-Wadan Zariya ne.

Saboda saukar Sarkin Zazzau Malam Ibrahim a gidan da aka gina masa (Asibitin Yara a yanzu) ya qara havaka unguwar sosai, ya kuma qara mata kwarjini don haka ne jama'a suka daina kiran garin da sunan unguwar leburori sai Tudun-Wada. Saboda Sarkin Zazzau yana da masauki a wannan unguwa, ba zai dace da a ci gaba da kiran unguwar unguwar leburori ba.

Da aka jima da kafa Tudun-Wada, sai Gwamna Clifford ya umarci lya Abdullahi da ya samu Sarki babba mai cika ido ya ba shi sarautar Tudun-Wada domin wannan sabon wuri zai havaka sosai mai yiwuwa ne ya fi qarfin Sarkin Tudun-Wada Kwasau nan gaba. Shi Kwasau, Allah Ya yi shi mutum ne gajere

---

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim, ran 25 ga Afriluu 1984.

mai qaramar qira. Don haka sai aka cire shi daga sarautar, 'Iyan Gari Abdullahi sai ya kawo Muqaddas daga Zariya aka ba shi sarautar Tudun-Wada, bayan an fitar da Kwasau.

Sarkin Tudun-Wada Muqaddas ya samu misalin shekaru uku yana sarauta, sai ga aike ya iso daga Zariya, cewa ana buqatar lya Abdullahi da muqaddashin lya Ibrahim da ke Maqera da Sarkin Barnawa Malam Guruza da Sarkin Kawo Abdullahi duk ana buqatarsu a Zariya, samun wannan aiken Sarkin Zazzau ke da wuya sai Sarakunan suka runtuma cikin dare suka bi jirgi zuwa Birnin Zazzau. Sun kwana gidan lyan Zazzau wanda ya ba su masauki, da safe wajen misalin qarfe tara na safe (9 a.m.), sai suka tafi wajen Sarki Ibrahim suka same shi da Razdan Keftin E.H.B. Laing.[1]

Razdan ya ce da Sarkin Kawo Abdullahi muna son garin ka ya cika da jama'a ko ka fara karvar haraji? Sarkin Kawo ya amsa da cewa ya karvi fam ashirin da biyar, har kuma ya aiko da su ga lyan Zazzau don a zuba su a Baitu-Mali. Sabon Sarkin Tudun-Wada Muqaddas, shi ma ya amsa tambayarsa da cewa ya karvi fam shida amma suna gida a Kaduna.

Mista E.H.B. Laing ya ce da su zai zo Kaduna zai kuma karvi kuxaxen don ya mayar wa talakawa, yaci gaba da cewa za a cire wa jama'arsu harajin shekaru biyar. A cikin waxannan shekaru kuma babu aiki. Baturen ya yi masu bayani da cewa an xauki wannan mataki ne saboda talakawa su wala, kuma garuruwan Sarakunan wato Kawo da Tudun-Wada da Maqera da kuma Barnawa su cika da jama'a sosai.[2]

Waxannan sabbin matakai da aka xauka tun a ranar 25/11/1924, aka xauki umarnin yinsa. Muddin jama'a suka zo Kaduna babu wanda zai zo cikin Sabon Garin Doka inda zai biya haraji, matuqar ga wurin da zai zauna inda babu haraji ko aiki. Wannan abu ya janye hankulan jama'a daga son zama a Sabon Garin Doka abin da Turawa ke buqata. Saboda haka sai Tudun-Wada ta fi ko'ina havaka da jama'a cikin hanzari.

An yi misalin sati biyu, sai ga Sarkin Zazzau Malam Ibrahim tare da Rasdan sun iso Kaduna inda suka zarce zuwa Maqera. A nan Maqera Sarkin ya aika aka kirawo Sarakunansa. Sarkin Kawo Abdullahi shi ne ya fara bayanin yadda ya karvi kuxin harajin da jama'ar da ya karvi kuxaden daga hannunsu. Aka duba wannan bayani nasa aka ga gaskiya ne, wannan abu sai ya faranta wa Sarkin Zazzau rai har ya sa masa albarka. Amma wajen Sarkin Tudun-Wada Muqaddas kuwa ba a samu su fam shida da ya faxi ba. Wannan abu da ya faru sai Sarki ya sa aka yi a Tudun-Wada cewa duk wanda ya biya kuxin haraji, to, ya fito, jim kaxan sai jama'a suka taru, aka ga cewa jimillar kuxi dai har ya kai fam tara.

---

[1] Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim, ran 25 ga Afriluu 1984.

[2] *Ibid*.

Ganin wannan abu da ya faru sai Sarkin Zazzau ya biya waxannan mutanen kuxinsu, amma shi Rasdan sai ya fusata har ya ce sai a kama Muqaddas don a hukunta shi. Sarki Ibrahim sai ya ce da shi a'a zai tafi da shi can Zariya, ai can ma kamar waqafi ne.[1] Wannan abu da Sarkin Tudun-Wada Muqaddas ya aikata shi ya sa aka tuve shi daga sarauta. Cire Muqaddas ke da wuya sai jama'ar Tudun-Wada suka kai kukansu cewa su Sarkin su na da suke so wato Kwasau. Sai aka dawo masu da shi ya ci gaba da sarautar Tudun-Wada har ya zuwa lokacin Sarkin Zazzau Jafaru.[2]

An fitar da Sarkin Tudun-Wada Kwasau a cikin shekarar 1940, saboda wata 'yar tangarxa da ta faru bisa rasixan haraji. Saboda haka Sarkin Kawo Muhammad xan Sarkin Kawo Abdullahi yana sarautar Kawo sai aka mayar da shi sarautar Tudun-Wada qanensa kuma Ibrahim Abdullahi aka naxa shi sarautar Kawo.[3]

Bayan Sarkin Tudun Wada Muhammadu sai Mallam Sule ya samu sarautar wannan gari, daga shi ne sai Malam Hayatu xan Sarkin Fada Yahaya ya sami Sarautar Tudun Wada. A wajen limanci Malam Muhammadu ne ya fara zama liman daga shi sai Malam Ali daga shi sai Malam Halliru waxannan limamai sun taimaka sosai wajen raya Addinin Musulunci a Tudun Wada. Akwai malamai masu yawa da suka ba da gudunmawarsu wajen havaka Addinin Musulunci. A lokacin babu wani babban masallaci duk a masallacin garin Kaduna dake Kano Road ake zuwa Sallar Juma'a.

Amma ana cikin wannan hali ne sai Malam Abu Mai Goro to bayarda rabin gidanta da ke 'Yar Kasuwa don a maida shi masallaci, wanda ya zama shi ne Masallacin Juma'a na farko a wannan gari daga baya ta bayarda gidan xungum don ya zama xakin Allah. Saboda haka sai jama'a suka sami sauqin zuwa Kano Road ranar juma'a tun da ga masallaci ya samu.

A shekarar 1978 da qungiyar *Izalatul-Bidia Wa Iqamatus Sunna* ta fito tana wa'azi sai aka samu rarrabuwar masallatai tsakanin 'yan wannan qungiya da 'yan xariqar Tijjaniya a garin Kaduna. An kuma sami bambancin fahimta wajen lokutan Sallar Juma'a da hamsus salawati. 'Yan Izala na Sallar Azahar da misalin qarfe xaya na rana, 'yan Xariqa na yin sallarsu da misalin qarfe biyu na rana. A dalilin haka ne sai idan 'yan Izala suka yi sallarsu da qarfe xaya sai 'yan xarika

---

1 Hira da Sarkin Unguwar Shanu Ibrahim, ran 25 ga Afriluu 1984.

2 *Ibid*.

3 *Ibid*.

suyi ta su da qarfe biyu duk a masallaci guda. Saboda haka sai aka riqa sallah kama-kama na juma'a da hamsussalawati.

Ana cikin wannan hali ne sai wani Bafilatani mai suna Alhaji Balan Kalaba ya soma gina sabon massallacin Tudun Wada a wani waje dake tsakanin Tudun-Nufawa da Tudun Wada. Alhaji Audu kwangila ya taimaka akagama gina wannan babban sabon Masallacin Juma'a. Ya kuma qara masa hasumiya sa'an nan ya qawatar da shi sosai. Shi ma wannan masallaci ana gama shi sai jama'a suka ci gaba da Sallah karva-qarba a cikinsa, kamar yadda ake yi a wancan tsohon masallaci. Amma wannan tsari sai ya riqa haifar da matsaloli daban daban. A dalilin haka sai aka ga ya kamata a raba masallatan tsakanin 'yan xarika da 'yan Izala.

An so a samu hargitsi wajen raba waxannan masallatai domin kuwa wace qungiya ce zata karvi sabon masallaci sai ya kawa taqaddama sosai. Daga qarshe sai hukuma ta shigo ta raba gardama. Ta baiwa 'Yan Xariqa sabon masallaci. Daga nan sai Liman Malam Halliru ya zama Limamin farko, da Malam Salisu, Na'ibi. Da Malam Salisu ya rasu ai aka naxa Malam Rufa'i Abduljalal ya zama Na'ibi. Da Allah Ya yiwa Liman malam Malam Halliru rasuwa, sai limancin wannan masallaci ya koma hannun Malam Rufa'i. A wannan lokaci sai aka naxa Malam Yusuf ya zama Na'ibi.

Tsofaffin zama Akwai mutane waxanda za'a kira tsofaffin zama a Tudun Wada, waxanda suka taimaka gaya wajen bunqasa wannan gari, akwai kaxan da za'a iya kawo wa: Ali Wanzami, Balarabe Maigadi, Tanko Wanzami, Magajin Aska Danladi, Sarkin Dillalai Hamza, Tambaya Wanzami, Ali Butu mai saran qashi, Sarkin Magina Muhammadu, Sule Algaita, Alhaji Mamman, Ali Audu Mijin Maidanko, Alhaji Muhammadu Armaya'u, Madaki Kwana-shuni.

A wajen kula da tsabtar gari da mahalli Malam Tanko Dubagari, da Malam Halliru Dubagari da Malam Habibu Dubagari sun taimaka sosai wajen wannan aiki Sarkin Pawa Gambo da Sarkin Pawa Gagarau sun bada gudunmawa wajen bunqasa sana'ar mahauta a wannan gari.

Garin Tudun Wada ya yi suna sosai a wajen mawaqa da maroqa a wancan zamani. Akwai mawaqa kamar Zabiya Hana, Adamu xan-nana, Yusuf Goyen baka, xangama Mai-Caji, Hanau Mai-Caji da Garba Mai tandu. Maroqa da suka shahara akwai, Ya'u Galadima, Sarki Abubakar Garba xan-Isyaku, Dogo mai molo, Mamman Gilaro, Garba xan Keftin wakili, Ado Galadima, Bera Maroqi, Haruna xanqaraye, Adamu Danvaure, Mamman na Zeena. A wajen makaxa

Sarkin Makaxa Akawu Labo da Sarkin Makaxa Lado mai kalangu, da Sarkin Makaxa Garba Mai kalangu duk sun yi fice a wannan sana'a, har da Tsoho xankwaci da Tanko Mai Kalangu.

Waxanda suka shahara a sana'ar bori kuwa sune: Mai Koko 'Yar-bori, Aminan Nadabo, Aminan xandabo, Mamman Xan Wayya, Abarshi Dogo Jikan A'i, Garba Mai Katako Kande Yargaruwa, Hauwa 'Yar Wamako da Kande Jos, '"Yar Umaru gyaxa mai sihiri. A vare aga biyu, a hure ki hau guguwa". A wajen harkar maganin Gargajiya akwai waxanda suka shahara kamar Shattu Maidanko, Auta Mai magani, da Malam Adamu Mai Kyanwa. Akasarin waxanda suka shahara a sana'ar maganin gargajiya kuwa Ningawa ne.

Kwanar Lami, Wannan kwana dake Tudun Wada ta samo suna ne daga wata shahararriyar 'Yar NEPU, qabilar Birom, mai suna Lami Filato. Ta Shahara wajen rawar Goge wadda ta wannan hanya ce qungiyar NEPU ke samun kuxin shiga. A wajen rawar Banjo ba kamarata, ta kuma yi qoqari gaya wajen nema wa jam'iyyarta kuxi. A lokacin ta zaune a gidan Adamu Mai Goro, sai aka riqa wa wannan kwanar zuwa gidan "Kwanar Lami Filato".

Mutanen Tudun Wada maza da mata a tsaye suke wajen riqe sana'a da ci da guminsu a wancna lokaci. Akwai Attajirai waxanda suka taimaka wajen havakar kasuwanci da sana'o'i iri-iri. Waxanda suke sanannun attajirai sune: Alhaji Adamu Gaga Mai goro, Alhaji Ahmadu Mai Goro, Hajiya Habiba Mai Azara, Shattun Kaila Mai Awo, alhaji Muhammadu Anni Mai Awo, Alhaji Sabo Mai Awo, Hajiya Ladi Mai Awo da Alhaji Musa Bola. A wancan zamani Hajiya Habiba Mai Azara da Shattun Kaila Mai Awo suna da qarfin arziqi sosai. Domin a wani lokaci da hukumar Tudun Wada ta nemi wasu quxi fam hamsin da gaggawa daga attajiran wannan gari. Wajen Hajiya Habiba Mai Azara aka same su bada vata lokaci ba.[1]

Hanyar Mota da Maqabarta

Da Tudun-Wada ta kafu, an fitar da layukanta an kuma sanya masu suna. Waxanda suka kafa allunan sunayen waxannan layuka kuwa su ne: Sule Zagu (Banufen Bida) da Audu Xanladan (Basakkwace) da Audu Ruwan Batur (Bazazzagi). A lokacin wannan aikin Haruna Xanqaraye ne ke bin su xauke da

[1] Hira da Malam Haruna Xanqaraye da Alhaji Muhammadu Xangoggo, tare da Alhaji Ladan Kwantagora, mashahurin ma'aikacin rediyo, a ran 28 ga Maris 2010

allunan ko *signboards*. Saboda haka su ne suka kafa wa kowane layi sunansa.[1] An sami fitattun layuka a gari kuma na havaka sosai kamar yadda ake so, sai ya zama ya kamata a yi hanyar mota da za ta haxa Tudun-Wada da garin Kaduna. Sai ma'aikatar Fidaburdi ta xauki nauyin wannan aiki, ta gina hanyar da ta haxa *King George's Way*, wato Sokoto Road a yanzu, da Tudun-Wada. An kammala aikin yin wannan hanyar ranar 20 ga Oktoban shekarar 1926. Saboda hanyar motar ta ratsa ta jirgi, sai da 'yan ma'aikatar Reluwe su masuka yi daven siminti da qofar kare mota bin hanyar in jirgi ya doso, 'yan Reluwen sun kashe fam ashirin da biyar da sulai goma domin wannan aiki na *Railway Crossing*.

Tudun-Wada tana qarqashin mulkin Zariya ne, kuma ita wannan hanya za ta daxa bunqasa wajen, sai Kantoma Mista Browne ya buqaci hukumar Zariya ta kawo taimakon kuxin aikin hanya, hukumar Zariya ta taimaka da kuxi har fam shittin.

Samuwar wannan hanya da ta haxa King George's Way da Tudun-Wada ta haifar da zirga-zirga daga cikin Kaduna zuwa Tudun-Wada. Saboda wannan ma har an samu damar gina gidan Gwamna a unguwar Badiko cikin hanzari. An gama gina gidan Gwamna a cikin shekarar 1928 amma an samu 'yan shekaru ba a tare a ciki ba. Wanda ya fara tarewa a wannan gida kuwa shi ne Sir Theodore Adams a lokacin varkewar yaqin duniya na biyu.

Da jama'a suka havaka a Tudun-Wada sai aka mayar da gonar Malam Rafa maqabarta. Ita wannan makekiyar gona, ita ce ta yi Kudu har wajen gadar jirgi daga Tudun-Wada. Tun daga bakin hanyar jirgi har ya zuwa bakin kogin Kaduna gonar Malam Rafa ce.

Jama'a mazauna Sabon Garin Doka da Tudun-Wada a wannan gona suke jana'izar mamaci. Idan mutum ya rasu sai a tafi da shi gonar Rafa a binne, don haka sai jama'a suka riqa cewa, "an-kai-wane-ko-wance gonar Rafa. " Wato dai ana nufin mutumin ya rasu ke nan. A wannan lokaci duk wanda aka ji an kai shi gonar Rafa sai ka ji an ce, Allah Ya ji qansa.

Da farko, Musulmi da Kirista duk a wannan gona ake jana'izarsu, amma cikin shekarar 1940, sai wani Malami mai suna Malam Tanimu Zariya ya kai kukan jama'a zuwa ga Mista Baker bisa wannan abu. Malam Tanimu ya ce da Kantoman, Musulmi da Kirista addininsu ya bambanta, yadda suke jana'izarsu duk sun bambanta. Saboda haka, bai kamata a bar su a maqabarta guda ba. Mista Baker ya yi na'am da wannan shawara ta Malam Tanimu, don haka sai aka mayar da maqabartar Kirista zuwa Kabalar Doki, su kuma Musulmi suka ci gaba da jana'izarsu a gonar Malam Rafa.[2] Da kuma Malam Tanimu Zariya ne aka kafa Tudun-Nufawa.

---

[1] Hira da Haruna Xanqaraye, ran 28 ga Maris, 2010

[2] Hira da M. Tanimu Zariya 15 ga Nuwamba 1984

Tudun-Nufawa

Dalilin kafa wannan unguwa ta Tudun-Nufawa kuwa shi ne, saboda yawan fashin da ake yi wa jama'a, idan za su qetaro daga Tudun-Wada zuwa Sabon Garin Doka ko kuma zuwa Zango inda ake cinikin dabbobi. Cikin xan wannan tsakani sai varayi suka riqa hana mutane saqat. Ganin wannan abu fa sai jama'a suka fara bayar da shawarwarin da gina gidaje a wannan yanki. Saboda haka sai jama'a suka bayar da filotai a wannan jejin. Idan mutane suka kafa gidaje a wannan wuri, za a yi maganin fashi a wannan waje ke nan. An fara bayar da filayen da iznin Sarkin Zazzau Jafaru.

Shi wannan wuri da ke tsakanin Zango da Tudun-Wada akwai shi da Tudu da kuma Rafi. A cikin shekarar 1948, an fara bai wa jama'a fili a kan tudun, waxanda aka fara bai wa filayen a wannan lokaci su ne: Malam Ilu, da Malam Tanimu Zariya, da Malam Yahaya Mai Lave-Lave, da Malam Yalwa Mai Kilishi, da Malam Sama'ila, da Yusuf Sadi, da Samanja Xan Wuta, da Alhaji Gwadabe Direban Gwamna, da Babaliyo Tela, da Musa Hamvago da Falmata Mai Tuwo, da Burai Xan Zaki, da Sarkin Pawa Nayaya da Xan Lagos Charlie. An bayar da wannan wuri bisa kowane fili mai faxin yadi hamsin da tsawon yadi hamsin (50 yds x 50 yds) a kwabo hamsin (50k). Wannan sabon wajen, da sai aka shiga yi masa laqabi da "Tudun Ilu Gangaren Mai Yalwa. "[1]

A cikin shekarar 1957 wasu Nufawa daga Bida sun je wajen Alhaji Aliyu Makaman Bida suna so su ma a ba su filaye don su yi gidaje a Kaduna. Sai Makaman ya ce da su, su tafi su nemo wajen da suke so a ba su filayen. Su Nufawa mutane ne ma'abota tudu, saboda a duk inda suke sun fi so su yi gidajen su a bisa tudu. Ganin tudun da unguwa ke kafuwa, sai suka bai wa Makaman labarin cewa, sun gano sabon wuri bisa tudun da ke tsakanin Tudun-Wada da Sabon Garin Doka (wato Yamma maso kudancin unguwar leburori ta da).

Shi ma wannan waje an riga an fara bayar da shi, domin akwai mazauna wurin kamar su: Malam Hassan Baduku, da Galadi Mai Doya, da Baqo, da Xanwawu Mahauci, da Sharubutu Direba, da Garba Mai Gyaran Agogo, da Alhaji Lawan Xan Sarkin Mutane, da Idi Xan Koli, da Malam Isa Xan Janhol, da Audu Mai-ata Mai Babban Soro, da sauran kuwa su ne: Ahmadu Zaruqu Banufe, da Xan Mami Xan Haya, da Malam Awaisu Banufe, da Alhaji Isma'ila Banufe, da Alhaji Manko, da Malam Sani Mai Qasa, da Haquri Sarki, da Tanko Mai Naso Tela, da Alamuna, da Malam Shehu Banufe Xan Kwangila, da Alhaji Ahmadu Mai Azara, da Sani Mai Awo.[2] Zuwan Nufawa wannan unguwar ya bunqasa ta.

Saboda haka ne ake kiranta Tudun-Nufawa a maimakon Tudun Ilu Gangaren Mai Yalwa. Tudun-Nufawa Kano da Tudun-Nufawa Ibadan duk bisa tudu suke.

---

[1] Hira da M. Tanimu Zariya ran 28 ga Nuwamba, 1984.

[2] Hira da Alhaji Alamuna ran 30 ga Nuwamba, 1984

Saboda Nufawa na son gidaje bisa tudu. Wajen shugabancin wannan unguwa, Malam Baqo mai Lallai shi ne ya fara yin Mai Unguwa. Daga shi sai Malam Lawal Banufe, sannan sai Malam Abdullahi Yusufu. Shi Malam Abdullahi, mutumin Xambatta ta qasar Kano ne. Shi ne kuma wanda ya zama Sarkin Tudun-Nufawa na farko.

Sarkin Tudun-Nufawa Abdullahi

An haifi Malam Abdullahi Xan Malam Yusufu Mai Ta-Annabi, a wani gari mai suna Barebari da ke kusa da garin Ajumawa a Qaramar Hukumar Makoxa ta Jihar Kano, a shekarar 1918. Mahaifinsa mutumne Karimi, wanda ya shahara wajen aikin qira da sassaqa, ya yi suna a wajen kyauta da sadaka domin haka ne ake masa laqabi da "Yusufu Mai Ta-Annabi. "

A lokacin da yake matashi, bai shiga aikin qira ba, sai ya shiga aikin gini da kasuwanci. Ya xan tava aiki a Kazaure da garin Dambatta daga nan sai ya tafi garin Jos a shekarar 1954. A wannan lokaci, wannan gari na tashe wajen aikin kuza. Saboda buxewar harkar kasuwancin kuza sai Kanawa su ka shiga sufuri da kasuwanci a wannan gari. A dalilin karuwar jama' a wannan gari, sai sanalar gini ta havaka sosai.

A wannan gari sai M. Abdullahi ya shiga aikin gini, inda ya yi suna a wannan sana'a. Daga nan sai ya taho Kaduna, ya zauna a Tudun-Nufawa, a shekarar 1958 inda yaci gaba da sana'ar gini. Da wannan sana'ar ta bunqasa sai ya haxa da dillancin gidaje.

Saboda qwarewarsa wajen hulxa da jama'a da kuma gaskiya da riqon amana sai jama'a suka zave shi ya zama Mai Unguwa a shekarar 1964, Sarkin Tudun-Wada Malam Bawa Hayatu ne ya naxa shi wannan muqami. Samun wannan muqami, ke da wuya sai jama'a suke ta yabonsa wajen halin haquri da adalci wanda Allah Ya huwace ma sa.

Saboda ganin hakane sai Malam Alu Magatakardan Sarkin Tudun-Wada, ya umarci Malam Bawa Hayatu da ya qara masa girma, saboda ya cancanci qarin girma idan aka yi la'akari da aikinsa da dangartakarsa da jama'a. Dalilin haka sai aka naxa shi Madakin Tudun-Wada a shekarar 1968, mulkinsa ya haxa da na Tudun-Nufawa da sauran unguwanni da ke qarqashin Tudun-Wada.

A shekarar 1974 ne a ka qara bunqasa Masarautun Kaduna. A cikin wannan sabon shiri za a qara faxaxa masauratar Tudun-Wada, a kuma qara mata daraja. Saboda hangen zuwan wannan shiri, sai Sarkin Tudun-Wada Malam Hayatu ya kira Madakinsa Abdullahi, ya ce da shi: "Madaki, saboda qwazonka da nagartarka da haquri da adalci zan sami qarin girma nan ba da daxewa ba. Saboda haka in na samu ci gaba, kai ne zaka hau wannan kujera tawa, ka zama Sarkin Tudun-Wada. Saboda gogewa a cikin sha'anin mulki da kuma gaskiya da riqon amanarka, ganin

kuma kyawawan halayenka ba a voye suke ba kowa ya sansu. Domin haka ne ka samu karvuwa ga jama'arka. "[1]

Wannan shiri nasa bai yiwu a haka ba. Saboda da aka naxa shi Hakimin Tudun-Wada da sunan sarauta "Iya " sai ya kira Madakinsa ya ce da shi: "Madaki a kan maganar Sarauta da muka yi a kwanan baya an sami wani shiri, an ba ni Dagatai biyar. Amma inda kake a Tudun-Nufawa kai ne Dagacinta. "[2]

An naxa M. Abdullahi Madakin Tudun-Wada, Sarkin Tudun-Nufawa, a cikin shekarar 1974 a lokacin da aka inganta sarautun gargajiyar Kaduna. Sauran waxanda aka naxa qananan Sarakuna a wannan lokaci su ne: Alhaji Bawa Hayatu lyan Zazzau kuma Hakimin Tudun-Wada yana da waxannan daga tai da Malam Shehu Sarkin Tudun-Wada da Alhaji Isa Sarkin Sabon Garin Tudun-Wada, da Malam Sunusi Sarkin Arewa (Unguwar Sunusi), da Malam Aliyu Sarkin Kurmin Mashi.

Da ya zama Sarkin Tudun-Nufawa, na farko sai ya qara qwazo wajen haxin kan al'umma musamman yankin mulkinsa ne yafi yawan qabilu iri-iri. Ya kuma tafiyar da mulkinsu cikin gaskiya da adalci saboda haka ne jama'a ke masa kirari da "Mai Tudu, Damo Sarkin Haquri. " Allah kuma Ya yi masa kyakkyawan taimako ya rabu da jama'a lafiya, yana ce masu Assalamu Alaikum suna amsa masa; "Alaikum Salam. " Wannan ya faru ne saboda Allah Ya yi shi ba mai son tara abin duniya ba ne, mai tsayawa ne tsayin daka, ya ga kowane mai haqqi an ba shi haqqinsa. Ya rasu a ran Talata 24 ga watan Afrilu na shekarar 1998. Ya rasu ya bar ya'ya shida biyu maza huxu mata. Sune: Yusufu, Hajara, Shuaibu, Zainab, Maryam da Asabe.

Mai martaba Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris, CFR, LLD, ya naxa babban xansa Dr. Yusuf Nadabo Abdullahi, Sarkin Tudun-Nufawa a fadarsa a ranar 13 ya watan Agusta na shekarar 1998. A wani shirin qara Dagatai domin faxaxa masauratar Zazzau, an raba Tudun-Nufawa kashi biyu. Mai martaba sai ya naxa qaninsa Alhaji Shuaibu Balarabe Abdullahi a matsayin Sarkin Dutse, a ranar 4 ga watan Mayu na shekarar 2005 domin ya shugabanci xaya yankin Tudun-Nufawa. Shi Sarkin Zazzau ba mai kashe gidan sarautar kowa bane sai dai idan gidan ne ya kashe kansa. Wannan ne zai tilasta samun wanda ya dace ya kuma karvu ga jama'a.

A lokacin Malam Abdullahi Yusuf Tudun-Nufawa ta bunqasa sosai. An kuma sa mi zaman lafiya a tsakanin Kabilu daban-daban. A wannan lokaci ne ya naxa limamin Tudun-Nufawa Malam Rabi'u wanda shi ne ya zama limamin unguwar na farko.

---

[1] Hira da Alhaji Alamuna ran 30 ga Nuwamba, 1984

[2] Hira da Sarkin Tudun-Nufawa Abdullahi a ran 13 ga Satumba 1984.

Unguwar Shanu

Sunan wannan unguwa ya samo asali ne daga shanun Gwamna. Tun a garin Dungurun ake kiwon shanun Gwamna, saboda su waxannan shanu na Gwamna, a kan yanka wa manyan Turawan mulki, su kan kuma ba da madara mai kyau. A wani lokaci kuma idan Gwamna Lugga na son ya tafi yawan shan iska, ya kan xaura wa shanun keke ya hau ya tafi 'yar kilisa. Mai kula da waxannan shanun kuwa wani mutum ne mai suna Ali, ban da kiwon shanu har lambun Gwamna yake kula da shi. Saboda wannan aiki nasa sai ana kiransa da suna Ali Gadinan Gwamna.

Bayan da Gwamna Lugga ya gano wajen da zai kafa gari, wato Kaduna sabuwar hedkwata, sai aka kwaso wani rukunin shanun tare da mai kiwonsu, tun kafin zuwan Dungurawa, aka ba su fili kusa da inda aka kafa gidan Gwamna Daga baya. Ali da shanun Gwamna, sai suka zauna a cikin wannan daji inda ya ci gaba da kiwonsu tun cikin qarshen shekarar 1911.

Dalilin kwaso waxannan shanu zuwa wannan waje cikin hanzari haka, ba shi da tabbas, amma mai yiwuwa don su taimaka ne wajen ba da alamar wajen da zai zama gidan Gwamna, wato dai inda Gwamna yake son yin gidansa, yin hakan zai taimaka wajen yin safiyo. Harila yau an ce kwaso waxannan shanu zuwa wannan daji zai taimaka wajen gane ko akwai ciwon dabbobi da qudan tsando ke haddasawa. Amma ko ma mene ne dalili, Ali da shanun Gwamna sun riga Dungurawa zuwa wannan sabon waje.

Ali Gadinan Gwamna ya ci gaba da aikinsa na kiwon shanu a hankali, sai shanun suka hayayyafa, jama'a kuwa sai zuwa wajen suke yi suna kafa gidajensu. Ana nan sai wajen ya zama unguwa, ana kuma kiran ta 'Unguwar Shanu'. Lokacin da aka gina sabon gidan Gwamna a wannan waje, sai ya ci gaba da aikinsa na lambu da ban ruwa ga fulawoyin gidan Gwamna.

Bayan da Ali mai shanu ya rasu, sai leburansa mai suna Sulaiman ya karvi aikin kiwon shanun, unguwar kuma ta zama unguwar Sulaiman mai Shanu. Amma lokacin da za a koma da gidan Gwamna Badiko a cikin shekarar 1928, sai aka kwashe shanun zuwa sabon gidan Gwamna amma unguwar sai ta ci gaba da havaka. Sulaimanu mai shanu ya samu misalin shekaru talatin yana wannan aiki kafin rasuwarsa.[1]

A shekaran 1940 wannan unguwa ta havaka saboda tarewar wani Kamfanin sojoji wato "Northern Regiment. " Mutane da yawa sun taso zuwa wannan unguwa saboda sojojin. Ko bayan shekarar 1942 da sojojin wannan Kamfani suka tafi yaqin *East Africa* unguwar bata bar havaka ba.[2]

---

[1] Hira da Sarkin Unguwa Shanu Ibrahim, ran 15 ga Satumba 1982.

[2] E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na 411

Lokacin da yaqin 'Hitler' ya varke, sai aka tashi mutanen Unguwar Shanu a mazauninsu na asali da ke kusa da tsohon gidan Gwamna, aka dawo da su Yamma da hanyar jirgi. Filin da suka bari sai aka yi 'yan gidajen sojoji ginin qasa da rufin ciyawa masu yawa don saukar sojoji. An yi waxannan gidajen har kusa da unguwar . Sunan wannan Barikin sojojin da Turanci, 'Kalapanzin Barracks'.

Bayan da yaqin duniya na biyu ya qare, sai aka sallami sojoji da yawa, don haka gidajen da aka gina lokacin yaqi, sai aka rushe su. A hankali sai wajen ya zama fili. An fara gina gidaje a wannan fili lokacin siyasar farko. Inda aka maida Unguwar Shanu, wato a inda take a yanzu, sai ta ci gaba da havaka cikin hanzari. Tsofaffin sojojin da aka sallama, sai da yawa daga cikinsu suka koma wannan unguwa da zama. Wanda ya fara sarautar wannan unguwa, shi ne Hassan Makama xan Sarkin Kawo Abdullahi. Magajin Gari Muhammadu Sambo ne ya naxa shi a cikin shekarar 1953.[1]

Unguwar Kanawa

Bayan shekaru uku da naxa Sarkin Kano Abdullahi Bayero, sai ya zo Kaduna don tattaunawa da Kantoman Kaduna Mista Browne. An ce a wannan zuwa da Sarkin ya yi, ya buqaci Kantoman da ya bade izinin a kwaso waxansu magidanta guda goma sha-biyar da iyalensu daga birnin Kano domin su bar masa garinsa, su kuma dawo Kaduna, Kantoman kuma ya yi na'am da wannan abu da Sarkin ya buqace shi da yi. An yi wannan shiri a lokacin Gwamna Palmer. A wannan lokaci kuma akwai buqatar zuwan jama'a Kaduna domin su fafa unguwanni, a wani shiri na yaqi da kudan tsando.

Bayan da Sarkin Kano Abdullahi ya dawo birnin Kano, sai aka kwaso waxannan magidanta a jirgi daga unguwanni daban-daban zuwa garin Kaduna. Su waxannan magidanta tare da iyalansu sun baro birnin Kano cikin shekarar 1927. Kafin isowarsu kuwa har an tanadi 'yan xakunan jinka a inda yanzu suka kafa wannan unguwa.

Alhaji Audu Kuludu mai gyaran fitila, iyayensa na cikin waxanda suka taso, shi kuma yana da shekara goma shabiyar da haihuwa a lokacin da aka kafa wannan unguwa. An yi komai a idonsa da kuma wayonsa. Saboda haka ya ba da shaidar cewa: "A cikin watan Safar ranakun Talata da Laraba, 13 ga watan Safar muka iso Kaduna a shekarar 1927. "[2]

Mista Browne sai ya tura Sarkin Hausawa Babale da Rejimanci Malam Baqo, zuwa tashar jirgin qasa don taryar waxannan baqin Kanawan, da suka kafa wannan unguwar, waxanda suke Kanawa ne saboda haka ne sai aka sa wa wannan unguwar, 'Unguwar Kanawa'. Wanda ya shugabanci wannan qungiya kuwa shi ne

---

[1] Hira da Sarkin Unguwan Shanu Ibrahim, ran 15 ga Satumba 1984.

[2] Hira da Alhaji Audu Kuludu, ran 14 ga Satumba, 1984.

Malam Shehu. Shi Malam Shehu daga Katsina ne aka maido shi ofishin Rasdan na Kano, saboda wani savani da ya shiga tsakanin Malam Shehu Usman da Sarkin Katsina Muhammadu Dikko.

Maqasudin tasowar waxannan Kanawa zuwa Kaduna, an cewai wata 'yar tangarxa ce ta faru tsakanin Malam Shehu Usman tare da magoya bayansa da Sarkin Kano Abdullahi Bayero, don haka ne ya buqace su da su bar masa garinsa. Amma an ce an kwaso su ne don su zo su taimaka wajen bunqasa garin Kaduna. To, kowane dalili ne ma ya taso su, su ne suka kafa wannan unguwa.

Su magidantan da suka kafa wannan unguwar an kwaso su ne daga unguwanni daban-daban da ke cikin birnin Kano. Mataimakin shugaban wannan ayari, shi ne Malam Baba Xan Barebari. Sunayen magidantan kuwa su ne: Malam Shehu Usman (Shugaba), da Malam Baba Xan Barebari (Mataimakin shugaba), da Malam Mijin Yawa Dukurawa, da Idi Dukurawa, da Malam Alhaji Dukurawa, da Sir'adu Durumin Kaigama, da Kauma Durumin Kaigama, da Malam Muhammadu Sakkwato Soron Xinki, da Garba Mai Ganga Soron-Xinki, da Abdulmumini Karofin Dala, da Malam Durhu 'yan Kwaxi, da Malam Habu Gwangwazo, da Baban Amina Tela Soron Xinki da Malam Haladu.[1]

Saboda waxannan jama'a sun sauka a baqon waje, sai Mista Brown ya ba da umarni da a riqa bai wa kowane mutum kwabo hamsin (sulai biyar) a kowane mako. Don haka kowace Talata ana biyan kowane mutum yaro da babba kuxin abinci sulai biyar. Sai da aka samu misalin shekaru biyu cur ana biyansu kuxin abinci ba tare da an sa su aiki ba, amma cikin tsawon wannan lokaci da yawa daga cikinsu sun sami sana'ar yi. Wasunsu su kan aika Kano domin su saro kayayyakin tireda, da yawa daga cikin su, sai suka shiga tallar alawa mai taguwa a cikin garin Doka. A wannan unguwa, sai da suka buxe makaranta, suka kuma gina masallaci, a hankali sai jama'a suka riqa zuwa zama a unguwar Kanawa.

Malam Shehu Usman daga unguwar Malladan, sai ya ci gaba da shugabancin jama'arsa, shi ne kuma mai unguwar farko a wannan unguwa. Shi da yake Malami ne kuma ya fahimci karatun boko da na arabi, sai ya shiga yi masu limancin sallah. Suna nan zaune cikin lumana da farin ciki, sai gobara ta varke a cikin shekarar 1932 duk unguwar ta qone baki xaya qurmus. Jama'ar wannan unguwar sai suka nemi taimako wajen hukuma, aka kuma yi masu kyakkyawan taimako.

Malam Shehu Usman, Allah Ya yi masa rasuwa a cikin shekarar 1934, mataimakinsa Malam Baba Xan Barebari sai ya karvi ragamar shugabancin wannan unguwar. Shi Malam Baba Xan Barebari daga unguwar Sanka aka taho da shi. Shi ma Allah Ya yi masa rasuwa a cikin shekarar 1965. A cikin waxannan

[1] Hira da Alhaji Audu Kuludu, yana da shekara 72 a lokacin, a ranar 14 ga Satumba 1984. Shi ya ba da sunayen jama'ar da suka kafa wannan unguwa.

shekaru ne, sai unguwar Kanawa ta bunqasa sosai da jama'a, qabilu daban-daban suka zauna a cikinta.[1]

Unguwar Sarkin Musulmi

A cikin watan Maris na shekarar 1931, aka yi safiyon filotai guda takwas a kan hanyar Kaduna zuwa Zariya, a shiyyar da ke Gabas da wannan hanya. Biyar daga cikin waxannan filotan gidajen na Sarakuna ne daga: lardin Sakkwato, da na Sarkin Ilori da kuma wataqila na Attah na Igala.[2] Kowane filin gida mai faxi ne sosai, yana da tsawo zira'i xari uku da faxin zira'i xari (300' by 300'). Tsakanin fili da fili kuma na da tsawon zura'i xari. Amma wannan waje sai ta zama Unguwar .[3]

A lokacin da Hassan Xan Mu'azu ya samu sarauta, sai Turawa suka sa aka gina masa masauki Arewa da Unguwar Shanu. Shi ne Sarkin da aka gina wa gida a wannan waje, don haka sai aka sa wa unguwar suna, 'Unguwar '. A hankali kuma sai aka riqa gina wa Sarakuna gidaje a wannan unguwa. An gina gidajen Sarkin Gwandu a zamanin Sarkin Gwandu Halliru Abdullahi, da Sarkin Yawuri Abdullahi, da Sarkin Argungun Muhammadu Sama, da Sarkin Zazzau Malam Jafaru da Sarkin Ilori Abdulqadir. Su waxannan Sarakuna su ne suka fara tarewa a gidajen da Turawa suka sa aka gina masu a wannan unguwa tasu.

Turawa sun sa an danqara wa Sarakunan manya-manyan gidaje, inda yake har akwai wajen kiwon dawaki da kuma xakunan 'yan gadi, amma sai suka hana kowa iznin yin gida a kusa da Sarakunan, hasali ma, wani lokaci 'yan gadin Sarkin, Turawa ke turo su. Sarakunan Hausa ba su saba da irin wannan zama ba, saboda duk inda suke zaune sun fi so su riqa jin xuriyar jama'ar su, kusa da su ba a keve su a bayan gari ba, domin wannan halayya irin ta Turawa ce. Don haka duk lokacin da Sarakuna suka zo taro a Kaduna, kuma aka kai su masaukinsua unguwar, sai su ji ba wai saboda an takura su.

Daga baya sai Sarakunan suka nemi a bar su su riqa zaunawa da 'yan fadarsu da kuma a bai wa jama'a filaye kusa da su, don idan an buqaci 'yan yin gyare-gyaren gidajensu, ba sai an taho da su daga nesa ba. Saboda wannan dalili, sai aka bar 'yan leburorin Sarakunan yin gidaje a wannan unguwa. A hankali kuma sai jama'a suka fara zuwa wannan unguwa. Cikin xan qaramin lokaci unguwar ta havaka da jama'a; malamai da sauran mutane.

Sauran Sarakunan Hausa kuwa sai aka yi masu masaukinsu, a cikin garin Doka, kamar su Sarkin Kano, da Sarkin Katsina, da Sarkin Daura, da Sarkin Kazaure, da Shehun Barno da Etsu Nupe.

---

1 Hira da Alhaji Audu Kuludu, yana da shekara 72 a lokacin, a ranar 14 ga Satumba 1984.

2 E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na 410

3 *Ibid*.

Wannan Unguwa da aka kafa sai ta ci gaba da bunqasa cikin hanzari. Daga shekarar 1954 sai Ministoci da manyan ma'aikatan gwamnati suka riqa gina gidaje a wannan Unguwa. A cikin hanzari sai wata Unguwa ta kafu wato Unguwar Ministoci ko *Minister's Quarters* a Nasarawa da ke kusa da wannan waje. Saboda haka sai Unguwar ta zama babbar Unguwa.[1]

Akasarin Sarakuna kamar Sarkin Kano, da Sarkin Zazzau da na lardunan Bauci sun sayi filayen gidajensu ne a Arewa maso Yammacin Sabon Gari wato dai-dai kan titin Kano da bakin kasuwa. A wannan waje ne suka gina gidajensu cikin hanzari.[2]

Sarkin Kano ya mallaki filotai guda biyu a kan titin Kano (plots AC1 and AC6); Shehun Barno ya sayi wani gini a kan filoti mai lamba Q3 a shekarar 1934. Amma wasu Sarakuna kuwa sun fi so su mallaki gidajensu a wajen Sabon Garin Doka.[3] Alal misali,, da Sarkin Gwandu, da Sarkin Argungu sun mallaki gidaje a kan titin Kaduna zuwa Zariya. Haka kuma Aku na Wukari, da Sarkin Lafiya, da Sarkin Nasarawa, da Sarkin Keffi a Unguwa Munci suka yi gidajensu. Sarkin Zazzau da Sarkin Bauci sun mallaki filotai a Tudun-Wada.[4]

Tun da aka fara taron Sarakuna a Kaduna a shekarar 1930, sai Turawan Mulki suka buqaci da su sami mahalli a Kaduna. Saboda haka daga shekarar 1931 zuwa 1954 Sarakuna Arewa kusan duk sun mallaki gidaje a Kaduna.

Masallacin Bello

A wata shekara ce Sardauna ya yi furucin gina masallacin *Hamsus Salawatu* a Unguwar, amma sai Alhaji Abubakar Gumi malaminsa da ke bashi shawara akan harkokin Addinin musulunci ya umarce shi da ya gina na Jumma'a, maimakon qaramin masallaci. Malamin ya bashi mai Gwari.

Wannan dalili shi ne idan shi Sardauna xin ya je sallar Juma'a a masallacin Layin Kano da ke Sabon Garin Doka, wani lokaci 'yan NEPU na yi masa ihu, wannan ta tilasta wa shi Sardauna xin zuwa sallar Juma'a a garin Rigacikun. Saboda nisan wannan gari daga Unguwar da kuma wahalhalun da jama'a ke samu wajen tafiya sallar Juma'a can, sai Sardauna ya yi na'am da shawarwari da Malam Abubakar Gumi ya ba shi, sai ya yi niyyar gina Masallacin Juma'a.

Amma Sardauna ya ce da Malam Abubakar Gumi, "a gina Masallacin Juma'a ba tare da an sanar da hukuma ba? " Don haka sai malamin ya tashi takanas ya tafi wajen Magajin Garin Kaduna Malam Muhammadu Sambo ya shaida masa shirin

---

1 NAK/SNP 17/4 13,801: *Sanitation in Kaduna*.

2 NAK, Prof. 30, *Accomdation for Chiefs in Kaduna*.

3 *Ibid*.

4 E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na 407

gina Masallacin Juma'a da Sardauna ke buqatar yi a unguwar . Magajin gari ya ce ai ba a gina Masallacin Juma'a kusa da gari, sai dai in nisansa da na gari ya wuce mil uku. Saboda wannan dalili, sai Alhaji Abubakar Gumi da Magajin Gari Sambo suka shigo mota daga Sabon Garin Doka zuwa Unguwar, inda suka gane nisan ya zarce mil uku. Saboda haka sai ya ba da iznin gina wannan masallacin na Juma'a. An gina masallacin a cikin shekarar 1961.[1]

An yi bikin buxe wannan masallaci a Kaduna. Babban baqon da ya buxe masallacin shi ne, Mai girma Wazirin Sakkwato, Alhaji Junaidu, a ran 26 ga watan Janairun shekarar 1962. Jama'a da yawa suka halarci wannan biki, waxanda suka haxa da Shugabanni, da Ministoci, da Sarakuna, waxanda suke halarta Kwas a harkokin Qananan Hukumomi a wannan lokacin a Kaduna. Sai suka sami wannan damasuka xunguma wajen wannan muhimmin biki.

Kafin ya qaddamar da buxe wannan masallaci, Alhaji Junaidu ya ce gina masallaci da kula da shi yana xaya daga cikin muhimmin ayyukan da Allah Ya umarci kowane Musulmi da yi. Ya ci gaba da cewa, Annabi Muhammadu (Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) da Halifofinsa sun baiwa wannan aiki muhimanci. Ya kuma godewa Firimiya domin bin wannan umarni na Ubangiji da kuma bin sawun kakanninsa a wajen aikin Allah (SWT). Wazirin Sakkwato ya cikasa bayaninsa da cewa, ya yi farin cikin amsa gayyatarsa da aka yi, don ya buxe wannan masallaci. Yana gama jawabinsa sai Sardaunan Sakkwato ya yi nasa.

A jawabinsa Firimiya ya nuna godiyarsa ga Allah (SWT) da ya yi shi Musulmi, daga cikin zuru'ar Annabi Muhammadu (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare ghi) da Shehu Usman Xan Fodio. Ya kuma gode wa Musulmi baki xaya da 'yan Nijeriya waxanda suka yi imani da Addinin gaskiya. Ya ce " musulunci ne ke haxa mutane iri-iri da suka bambanta ta jinsi da launi a wajen Ibada ga Ubangiji. " Firimiya ya yi nuni da qaramin Jakadan Haxaxxiyar Jumhuriyar Qasar Larabawa wato *United Arab Republic* (U.A.R), da wasu ma'aikatansa da ke cikin masallaci a lokacin, inda ya ce imani ya sa su dulmiya cikin ayyukan al'ummar Musulmi.

Alhaji Abubakar Gumi wanda a lokacin shi ne Muqaddashin Alqalin-Alqalan Jihar Arewa, shi ya gabatar da Wazirin Sakkwato, ya kuma bayyana cewa Malam Modibbo Muhammadu Girei, tsohon xalibin Makarantar Arabiya, daga lardin Adamawa shi aka naxa Limamin wannan masallaci. Daga nan sai ya miqa wa limamin makullin masallacin da wata adaka xauke da littattafan Alqur'ani masu yawa. Malam Abubakar Gumi ya ce za a bar masallacin a buxe don xalibai su zo su riqa karatu.[2]

---

[1] Hira da Sheikh Abubakar Gumi, a ranar 19 ga watan Janairu 1986.

[2] Nigerian Citizen, No 1,007, Laraba, January 31, 1962

Wannan masallaci shi ne babban masallaci wanda ba sallar Juma'a kawai ake yi ba, har da sallar Idi. Kuma a kowane watan Azumi, Sheikh Abubakar Mahmoud Gumi yana yin wa'azi, jama'a daga ko'ina a qasar nan suna zuwa garin Kaduna don jin wa'azin nasa a cikin wata mai Albarka, wato, watan Azumi. Sardauna ya sa wa masallacin sunan ka kansa, Muhammadu Bello don haka ake kiransa Sultan Bello *Mosque*. Malam Muhammad Girei shi ne limamin masallacin na farko.

Abakpa

Wani tsohon soja mai suna Abarshi ya tashi da iyalansa daga layin Haxeja a cikin shekarar 1931, sai ya komo wani wuri kusa da Unguwar Shanu, inda ya gina gidaje biyu. A nan Abarshi ya zauna da iyalansa da 'ya'yansa guda shida, su ne Audu, da Wada, da Salihu, da Isa, da Tarihu da Ai'shatu.

A hankali sai aka sanya sunansa, ana kiran wannan wuri "Unguwar Abarshi " jama'a sai zuwa wajen suke yi suna kamafilaye suna gina gidaje. Wata tsohuwa mai sayar da giya sai ta zo Unguwar Abarshi, ta ci gaba da yin sana'arta ta sayar da giya, ita dai wannan Buzuwa mai sayar da giya, sai ta yi suna har unguwar ana yi mata laqabi da Unguwar Buzuwa. Jama'a daga unguwanni daban-daban sai su zo unguwar 'Yar Buzuwa don shan giya.

Ita wannan unguwar Abarshi, sai ta ci gaba da havaka cikin hanzari, amma bayan qarshen yaqin duniya na biyu, sai baqin sojojin Bakali suka daxa bunqasa wannan unguwa. Daga baya sai unguwar Abarshi ta koma ana "kiranta Abakpa bayan shekarar 1945.[1]

Akwai wata tsangayar Leburori da ke Tashar Doka wato "Kaduna North Station, " wadda ta fara havaka da zata zama wata babbar unguwar, sai aka ba su filaye a Abakpa. Haka suma mutanen 'yar Buzuwa da ke kusa da su, an tashe su sun koma Abakpa. Saboda haka sai wannan gari ya qara bunqasa sosai. Da aka tashi mutanen 'yar Buzuwa sai aka gina Babban Asibitin Soja a Kaduna da ake kira Asibitin 44.

Mazaunan farko ma'aikata ne da suka taso daga barikin sojoji na Recce York Barrack da ke wajajen *Lugard Hall*, da barikin Ethiopia Barrack da ke wajen titunan Banki da Sakkwato wato 'Bank and Sokoto Roads'. Akwai kuma tsofaffin sojoji da yawa da suka taso zuwa wannan Unguwa. Haka kuma akwai leburori da ma'aikata daga sassa daban-daban na wannan waje. A shekarar 1942 mazauna gidan haya a wannan Unguwa na biyan sulai biyu da sisi zuwa sulai uku (2/6d to

[1] Hira da Malam Muhammadu Mai 'Yam makaranta, ran 30 ga Nuwamba 1984.

3/-) a kowane wata. Saboda rahuwar kuxin haya, jama'a da yawa sun taso kwararo zuwa wannan unguwa.[1]

Unguwar Rimi

A cikin shekarar 1912 ne, lokacin da Dungurawa suka iso masaukin da aka yi masu a wani wuri Yamma da tashar Doka, wato Kaduna "North Station " daga nan ne sai baqin jama'a suke varkowa daga wurare daban-daban suna zama a Arewacin wannan tashar ta jirgi. Bayan da Dungurawa suka tashi zuwa Sabon Garin Doka, sai wani xan qaramin gari ya fara kafuwa a Arewacin tashar Doka, Gabas da masaukin Dungurawa. Shi wannan xan qaramin gari da Hausawa suka kafa, sai aka sanya masa suna garin Doka.

Amma a lokacin da aka gamafilan xin garin Kaduna baki xaya, kuma aka gama aikace-aikacen ginin sabuwar hedkwatar, sai ya zama tilas a tashi mutanen garin Doka zuwa wani wuri sabo. Sai aka tashesu bayan an biya su diyyar gidajensu waxanda duk ba su kai gidaje guda goma ba, aka kuma ba su fili can wajen gari kusa da rafin Rimi.

An sanya wa wannan wuri da mutanen Doka suka kafa suna 'Unguwar Rimi', saboda wani qaton itacen rimi da ke Gabas da garin. Shi wannan itacen rimi, shi ya sanya ake kiran rafin da ke kusa da shi Rafin Rimi. An kafa wannan unguwa a cikin shekarar 1915.

Hausawan Doka da suka dawo wannan sabon wuri, sai suka rabu kashi biyu. Wasu suka zauna yankin Arewa, wasu kuma suka zauna a yankin Kudu. A lokacin xan daji ne ya raba su a tsakani. Daga nan sai aka shiga kiran mazauna waxannan wurare 'yan Unguwar Kudu, ko "Rimi Fulani " da 'yan Unguwar Arewa ko "Rimi Hausa. " Saboda yawan waxan Kabili da ke zaune a waxannan yankunan. A hankali sai unguwannin biyu suka haxe, amma har yanzu suna nan da waxannan sunaye, Unguwa Kudu da Unguwar Arewa.

Zuwan su wannan sabon wuri, sai jama'ar garin suka shiga sana'ar sayar da itacen azara wanda su kan samo a kurmin daji ne da ke tsallaken kogin Kaduna da ke Gabas da garinsu. Wannan sana'ar azara ta bunqasa a wannan unguwa, a wannan lokaci, don mutanen Sabon Garin Doka xin, a wajensu suke sayen itacen azara. Saboda alherin da suke samu a wannan sana'a, shi ya sa ba su damu da aikin noma sosai da sosai ba sai daga baya.

Waxannan wurare sai suna havaka a hankali. A shekarar 1951 yawan mazauna vangaren Arewa sun kai xari da hamsin da bakwai (da yara talatin da tara), xaya vangaren Kudu kuwa mutanen sun kai yawan xari da talatin da takwas (sun haxa da yara hamsin da biyar). Yawan gidaje a wannan shekarar kuwa ya kai yawan

[1] E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation*, shafi na 412

gidaje tamanin (80 houses); guda arba'in da huxu a Unguwar Arewa (ko Rimi Fulani) da guda talatin da takwas a Unguwar Kudu (ko Rimi Hausa).

A kan samu cunKwason jama'a a waxannan gidaje wanda ke haifar da qazantar mahalli. Saboda haka ne ma Hukuma ta yi wani shirin tada waxannan unguwanni zuwa wani waje da ke kusa da kogin Kaduna.[1]

Da yake Unguwar Rimi tana qarqashin Kawo ne, sai ya zamana masu unguwanninta bayin Fulani ne da ake naxo su daga Kawo Haka kuma limamin Kawo ke zuwa wannan unguwa wajen raxa suna da xaurin aure da kuma jana'iza.

Limamin Kawo da ke zuwa Unguwar Rimi idan irin waxannan hidimomi sun samu, shi ne wani babban Malami mai suna Liman Na Jura. Ya daxe yana limancin Kawo bayan rasuwarsa ne sai xansa Malam Zakari ya samu limancin Kawo, shi ma ya kan zo Unguwar Rimi idan wata buqata ta wajen Malamai ta zo. 'Ya'yan wannan limami su ne suke limanci a Kawo. Kamar su, Malam Tanko da Malam Musa har ya zuwa Malam Muhammadu Ja'e xan Takwai.

Unguwar Rimi ba ta samu limamin kanta ba sai a cikin shekarar 1939, a lokacin da wani babban Malami Bakatsine mai suna Malam Isa Mai Doki ya zo wannan unguwa ta Rimi. Zuwan sa ya havaka unguwar, saboda ya gina masallacin farko da babbar makaranta da ake koyarwa. Shi Malamin Sarakuna ne, saboda bunqasarsa ne ma jama'a daga wurare da dama ke zuwa wajensa.

Ba a jima da kafa Unguwar Rimi ba, sai wata tsohuwa mai suna Kaka ta taso daga Layin Gwandu da ke Sabon Garin Doka ta zauna a wannan unguwa. Ta zauna kusa da wani itacen rimi sa'anan akwai rijiyar garin baki xaya kusa da gidanta. Zuwan wannan tsohuwa sai ta ci gaba da sana'ar sayar da goro da kayan marmari irin na da. Qofar gidanta sai sannu a hankali ya zama dandali na samari da 'yan mata ke gaxa. Idan an yi baqon mawaqi, to, a qofar gidan wannan tsohuwa zai yi wasansa. Nan da nan sai aka sa wa wannan dandalin wasa "Qofar Kaka, daga nan sai wajen ya zama "Qwarkaka " da wannan suna ake kiran wannan wuri har yanzu.

Wajen shugabanci kuma, bayin Fulani ke shugabancin Unguwar Rimi da farko, mai unguwa na farko shi ne Mai Unguwa Dogo na Gudje daga shi sai Albarka Targaba, sauran waxanda suka yi masu Unguwa su ne Audu Qato da Mamman na Jaji da Alhaji Yakunu Zariya har ya zuwa Mai Unguwa Xan Baqi. Hakimin wannan gari a lokacin rubuta wannan tarihi shi ne Alhaji Muhammadu Labo.

Mazaunan farko a wannan unguwa, sun sha wahalhalu masu yawa. A lokuta da yawa a kan tashesu su tafi can bayan-gari su zauna na wani xan lokaci. A duk lokacin da 'yan Sanda za su koyi harbi a buzayen da ke kusa da wannan unguwa.

---

[1] NAK SNP 17/14 13,80: *Sanitation in Kaduna*.

A kan ba su wani xan kofi idan hakan ta faru. Ana xaukar wannan mataki ne don tsoron kada harsashi ya yi masu varna.[1]

An yi qoqarin tashin wannan unguwa xungurungum saboda Turawa ba sa son xuriyarsu, saboda gidajen Turawa da ke wajen jefi-jefi. Su Turawan ba sa son hayaniyar jama'ar Unguwar Rimi, don haka suka ga babu abin yi sai a tashe su baki xaya. Maganar tashin unguwa ya yi zafi sosai a lokacin Kantoman Kaduna, Mista McCullum, amma duk shirin da aka yi sai Allah Ya warware shi har ya zuwan Firimiya.

A lokacin Sardauna wani Injiniya Bature ya kai maganar tayar da Unguwar Rimi ga shi Firimiya. Amma da jin wannan kalami na Injiniya sai Sardauna ya harzuqa ya kuma soki shirin da kakkausar murya. Wannan ta sa mazauna Unguwar Rimi suka huta da barazanar tashin su. Alhaji Sadau Usman ya yi matuqar qoqarin ganin shirin tashin unguwar ya ci tura. Shi ne wanda daga baya ya zama shugaban tsohuwar hukumar Kaduna. Wani attajiri mai suna Alhaji Wada Usman ya taimaka wajen bunqasar unguwar ta fannin kasuwanci.

Unguwar Munci

Qabilar Tiv ko kuma Munci sun yi tarzoma a garin Gboko wanda ya sa Turawa suka cire Sarkinsu daga mulki aka kai shi Kaduna a cikin shekarar 1926. Turawa sun gina wa Sarkin Munci xin gida a wani wuri da ke Gabas da Unguwar Rimi kuma tsallaken Rafin Rimi. A wannan wurin, sai Turawa suka yi wa Sarkin gida inda ya zauna tare da iyalansa har tsawon shekaru bakwai, sannan aka bi umarnin komawa da shi Gboko. Amma Kantoma, Mista Browne ya sanya aka riqa biyansa sulai bakwai, kuma iyalansa kowane na da sulai biyu a kowane mako. Zuwansa wannan wuri sai aka sa wa wurin suna "Unguwar Munci. "

A cikin shekarar da aka kawo wannan Sarki, sai aka buxe hanya da ta haxa wannan unguwa da Unguwar Rimi da Unguwar; sannan aka kuma gina babbar gadar Rafin Rimi saboda zirga-zirga tsakanin Unguwar Rimi da Unguwar Munci ta sauqaqa.

Rafin Rimi ya faro ne daga Batare da ke Unguwar Shanu, sannan yaketo Gabas da Unguwar Rimi ya kuma haxe da kogin Kaduna. Ya zama wajibi a yi wa kogin gada a Gabas da Unguwar Rimi, saboda haka ne ma shi wannan rafi ne mai zurfi sannan itatuwan gora sun fito birjik a gefensa.

Unguwar Munci ta bunqasa sosai har ya zuwa lokacin Magajin Gari Sambo. A zamanin Magajin Gari ne aka ta so da su mutanen Unguwar Munci xin aka dawo da su cikin Unguwar Rimi. A inda aka ba su filayen gina gida, shi ne ya zama sabon gida a cikin Unguwar Rimi a yanzu, filin da suka baro kuma aka yi gine-gine masu qayatarwa.

---

[1] Hira da Alhaji Usman Wada a watan Janairu na 1985.

Unguwar Badiko

An kafa Tudun-Wada, sai a wannan lokaci jama'a suka shiga fafutukar neman filayen gidaje. A cikin shekarar 1925, sai wani Malami (tare da almajiransa), ya fita ya kafa 'yar tsangaya a wani wuri da ke Arewa da Buzaye. A hankali sai unguwa ta tashi a wannan sabon waje. Shi wannan Malami Bakatsine ne mai suna Badiko, ya buxe babbar makaranta, aka kuma sa wa unguwar sunansa, wato "Unguwar Badiko'. Tana tashen havaka ke nan, sai aka tashi wannan unguwa, saboda za a gina gidan Gwamna a cikin shekarar 1928.

Saboda Gidan gwamnan da aka gina a wannan unguwa ta Badiko sai ya baiwa wannan waje kwarjini. Mafi yawan Gwamnonin Arewa sun zauna a wannan gida. Daga qarshen siyasar farko sai Gwamnonin Jihar Kaduna suka zauna. Amma ba kowane Gwamna ne ya zauna a cikinsa ba.

Garin Kaduna ya qasaita cikin hanzari, unguwanni sun cika maqil da jama'a saboda haka sai wannan gari ya zama kamar Arewa, ya zama gari mai bambanci da ban mamaki. Abubuwa biyu sun qara qawata garin da jin daxi da annashuwa. Na farko shi ne kafa Gidan Rediyo na biyu kuma shi ne kafa Gidan Rediyo mai Hoto. A matsayin Kaduna hedkwatar Arewa ne, ya baiwa wannan gari, ba abubuwan jin daxI da annashuwa ba kawai, har ma da na ci gaban xan-Adam.

KASHI NA TARA

Kaduna Hedkwatar Arewa

A ranar biyar ga Janairun shekarar 1917 aka kammala tasowa daga Zungeru zuwa Kaduna sabuwar hedkwatar Lardunan Arewa wato "Northern Provinces. " A shekarar 2007, Kaduna ta cika shekaru casa'in (90 years) da kafuwa. A shekarar 2017 garin zai cika shekara xari da kafuwa. Amma tun fil azal wannan gari Gwamna ke mulkinsa. Akwai sunaye manya guda biyu waxanda ke manne da wannan gari. Gwamna Lugga mashahurin Baturen da ya kafa Nijeriya ya kuma kafa garin Kaduna da, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato wanda ya bunqasa garin don mazaunansa su sami ci gaba da walwala tare da wadatan zuci.

Manyan-manyan Turawan mulki sun zauna a Kaduna, a matsayinta na hedkwatar Nijeriya ta Arewa. A wannan gari ne ake jan ragamar mulkin wannan makekiyar qasa, tun daga ranar 16 ga watan Nuwamba na shekarar 1917 lokacin da gwamnatin Mulki ta tare a wannan sabuwar hedkwata daga Dungurun, har ya zuwa 1 ga Oktoba na shekarar 1960, lokacin da Nijeriya ta samu mulkin kai.

Gwamna Lugga ya karvi shugabancin Yankin Arewa wato *Northen Proitectorate* a matsayin Babban Kwamishina, wato "High Commissioner " a cikin farkon shekarar 1900. Yana uqe da wannan mukami ya zuwa shekarar 1907 aka turo E.P.C. Girouard shi ma a matsayin *High Commissioner*. Turawa ne ke riqe da wannan muqamin har zuwa ranar 19 ga watan Maris na shekarar 1908, lokacin da aka sauya sunan muqamin jagorancin Arewa ya zuwa Gwamna kuma babban Kwamandan Sojoji wato "Governor and Commander In-Chief. " E.P.C. Girouard da H.H.J Bell suka zama Gwamnoni, shi kuma F.D. Lugga ya zama Gwamna-Janar a shekarar 1912. Waxanda suka zama Leftana Gwamna ko "Lieutenant Governor " har ya zuwa 1932, su ne; C.L. Temple, da H.S. Goldsmith, da W.F. Gowers, da H.R. Palmer, da C.W. Alexander da Vacant.

Daga shekarar 1933 sai muqamin shugabancin Arewa ya sauya ya koma hannun Cif Kwamishina "Chief Commissioner. " Waxanda suka riqe wannan muqami har ya zuwa shekarar 1951 su ne; G.S. Browne da T.S. Adams, da J.R. Patterson da Eric Thompstone. Bayan haka ne mulkin Arewa ya koma qarqashin Leftanan Gwamna a shekarar 1951, waxanda suka riqe wannan muqamin su ne: Eric Thompstone da Sir Bryan Sharwoodsmith har ya zuwa shekarar 1951, lokacin da muqamin ya zama na Gwamna.

Waxanda suke riqe muqaman Gwamnonin Arewa daga wannan shekarar su ne; Sir Bryan Sharwoodsmith, da Sir G.W. Bell, da Sir Muhammadu Sanusi (gwamnan riko) da Sir Kashim Ibrahim, da Manjo Hassan Usman Katsina, wanda shi ne gwamnan Jihar Arewa na qarshe. Waxanda suka riqe muqaman Sakatarorin

mulkin Arewa daga farkon shekarar 1900 har ya zuwa shekarar 1936 su ne; Mark Kerr da M.H. Poer Bereford, da C.L. Temple da, G.R. Mathews, da G.S. Browne da, G.J. Lethem da A.E. Veer Walwyn, da P.G. Harris, da J.R. Patterson, da E.S. Pembleton.

Mai girma Gwamna Lugga a lokacin yana Gwamna Janar na Nijeriya ya ba da umarnin tasowa zuwa Kaduna daga Zungeru tsohuwar hedkwata. Ya yi kuma niyyar maida wannan gari hedkwatar Nijeriya baki xaya. Daga gidansa da ke misalin yadi xari biyar (500 yds) tsakaninsa da *Lugard Hall*, wannan mashahurin gwamnan ya yi mulkin Nijeriya daga shekarar 1913 zuwa 1918. Amma gidan gwamnan Arewa na farko wato *First Governor's Lodge* daga shekarar 1913 na kan kusurwa inda layin *Independence Way* ya haxe da Wharf Road. Haka kuma wannan tsohon gidan gwamnan Arewa sai ya zama masaukin Firayim Ministan Nijeriya, Alhaji Abubakar Tafawa Valewa a duk lokacin da ya zo Kaduna. Wannan gida na kallon tsohuwar Sakatariya. Amma wannan tsohon gida an maida shi *Ministry of Health*, wato Ma'aikatar kula da Lafiya. A kusa da *Prison Yard* ko gidan waqafi a nan ne aka gina Gidan Kulob na Afrika wato *African Club* na farko a Arewa.

An daxe ana ciza yatsa saboda rashin cimma nasarar maida Kaduna hedkwatar Nijeriya. An kuma daxe ana alhinin rashin samun babbar tashar jirgin ruwa a Arewa. Wannan babban rashi ya kawo wa Arewa wani tarnaqin hana bunqasa da ci gaba ta fuskar ciniki da sauqaqa sadarwa. Tashar jirgin ruwa da ke Baro ita ce Arewa ke gadara amma ba za ta iya xaukar jiragen ruwa manya ba. Saboda haka ne ma ya sa idan fasinsojoji sun taho ta teku daga qetare sai a saukesu a Forcados. Daga nan sai su shiga qananan jiragen ruwa, *Steam Wheelers* su biyo kogin Kwara inda za a yi tafiya mai nisa zuwa Mureji, wani gari da ke mahaxar kogin Kwara da Kogin Kaduna, wanda yake da nisan mil xari huxu da hamsin da tara (459 miles) daga garin Forcados.

Amma wahalar bata tsayanan ba. Daga garin Mureji, sai matafiya su shiga qananan kwalekwale su kuma yi tafiyar mil tamanin da biyar (85miles) akan kogin Kaduna zuwa wani gari da ke kusa da Dungurun da ake kira Gwarjiko. Daga wannan gari kuma, sai a shiga jirgin Qasa zuwa hedkwatar Arewa. Saboda rashin babban kogin da ya shigo Arewa sosai, wanda kuma zai iya xaukar manyan jiragen ruwa, saboda haka sai aka ba da fifiko da hanyar jirgin qasa daga Baro zuwa Birnin Kano.

Har yanzu rashin babbar tashar jirgi a Arewa babbar illace mai dakushe ci gaba. A wannan zamani na ci gaba da aka samu a ilimin kimiyya da fasaha tare da ci gaba wajen sadarwa, ai qaramin kogi ana iya faxaxa shi. Haka ma ana iya sauya wa kogi hanya idan yin haka zai kawo ci gaba. Saboda haka ne ma Gwamnatoci da su ka shuxe suka yi qoqarin yashe tashar jirgin ruwa ta Baro. Domin manyan jiragen ruwa daga teku su riqa isowa kai tsaye zuwa wannan tasha. Daga wannan

tasha kuma sai kaya da fasinsoji su bi jirgin qasa daga Baro zuwa Kano ba tare da sun fuskanci wasu wahalhalu ba. Amma an sami ci gaba a kan wannan gwagwarmaya, a shekarar ta 2007, Mai girma Shugaban Qasa Alhaji Musa Yar'adua ya ba da kwangilar yasar tashar jirgin ruwan Baro. Babu shakka wannan wani babban mataki ne da zai kawo ci gaban Arewa. Wata rana na zuwa har Kogin Kaduna ma sai an yashe shi don a samu shigowar jiragen ruwa cikin Arewa sosai da sosai.

Gwamna Lugga ya jajircewajen maida Kaduna hedkwatar Nijeriya. Saboda ganin hakan ya cimma tura, sai Sardauna shi kuma ya jajircewajen ganin Kaduna ta bunqasa sosai a matsayin farfajiyar tafiyar da Mulkin Arewa. Sir Ahmadu Bello, ya qayatar da wannan gari da gine gine na zamani ya kuma bunqasa shi da masana'antu da makarantu har da wajen wasanni domin ci gaban Arewa da jama'arta. Daga gidansa da ke Arewa House da ke Unguwan Nasarawa (a wancan zamani) wadda ake kira Unguwa a yanzu) a kuma matsayinsa na Firimiya anan ne ya tafiyar da da mulkin Arewa da adalci wanda ya zama abin koyi har yanzu. Ba garin Kaduna ya bunqasa ba kawai, a'a sai da ya tsaya tsayin daka ya ga an ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa a wata gwagwarmayar da ya yi wa laqabi da, "Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, wato "*Northernisation Policy*. "

Saboda ya lura da cewa matukar 'yan Kudu suka mallake komai da komai, a hannunsa babu shakka za su maida 'yan Arewa qyale-qyale huhun-ma-ahu. Wannan shi ne dalilin da ya sa wannan Gwarzo xaukar wannan gwagwarmaya. Kaico! Sai garma ta karye da sauran aiki. An kashe Sir Ahmadu a shekarar 1966, a wannan shekarar kuwa Kaduna na da shekaru arba'in da tara (49) da kafuwa. Amma tun kafin Sir Ahmadu ya yi shahada, an sami ci gaba ta fannoni masu yawa a wannan gari wanda ake wa laqabi da Kaduna Garin Gamji.

A ranar Alhamis 5 ga watan Janairun shekarar 1967, garin Kaduna yacika shekaru hamsin da kafuwa. A wannan rana ce Editan Jaridar *New Nigerian*, ya taya wannan gari murnar cika shekaru 50. Editan ya ce:

"Muna taya mutanen Kaduna murnar cikar garin shekaru hamsin, a matsayin hedkwatar Arewa. Kaduna ita ce cibiyar gwamnatin Arewa tun kafuwarta. Ta kuma yi daban da kowane gari a Arewa.

"Gwamna Lugga wanda ya qirqiro kafuwarta, ya hangi cewa hedkwatar mulki ce ba ga Arewa ba har ma ga wannan qasa ba ki xaya. Wannan hange nasa kuma ya yi tasiri sosai.

"Kaduna ta zama cibiyar tafida mulki xauke da jama'a masu yawan dubu dari da hamsin (150,000). An gina masana'antu masu yawa waxanda ke ba da aiki ga ma'aikata qwararru maza da mata da kuma qananan ma'aikata.

"Mun yi imani da cewa shugabannin wannan gari za su yi alfahari da ganin bunqasa da ci gaban da aka samu. Muna ji kuma Kaduna na buqatar qarin ababen

more rayuwa. Ba ma kuma shakka, gwamnati za ta jajircewajen ganin ta maida Kaduna dai-dai da hedkwatar da ta dace da zamani.

"Kaduna na qara bunqasa da yawa jama'a wannan ya sa qarin mahalli da kula da lafiya su ka zama abubuwan lura da gaggawa. Muna kira ga gwamnati da ta qara gina gidajen haya masu rahusa waxanda kuxinsu ba zai qwamama wa jama'a ba.

"A kuma kula da matsalolin asibitoci da guraren shan magani. Muna murna da ganin ana ba da magani da asibitoci kyauta a Kaduna sai dai a wasu matsololi marasa yawa. Amma ya batun tsabtace gari? Ya kamata a kawo tsarin zubar da shara da bayangida irin na zamani. "Ya kuma kamata a hana zaman jama'a a wurare marasa tsari. A kuma qara wuraren shaqatawa da motsa jiki. Qarin lafiya ta ta'allaqa ne akan tsabtar mahalli. Zai fi dacewa a kashe kuxi wajen ababen motsa jiki don qarin lafiya fiye da a kashe su a asibitoci wajen sayen magani in jama'a sun kamu da ciwo.[1]

A cikin wannan gaisuwar taya murnar shekaru hamsin, Editan ya fito da matsololin da ke addabar jama'ar Kaduna a wancan zamani. A lokacin yawan jama'ar dubu xari da hamsin (150,000) ne kacal. An yi maganar masana'antu don a baiwa jama'a aiki, da maganar qawatar da gari da gine-gine irin na zamani da gidajen haya masu sauqin kuxi, da kula da lafiya da asibitoci. Haka kuma an yi maganar tsabtar mahalli da hana zaman cunKwason jama'a tare da baiwa jama'a ababen more rayuwa. Har ila yau, an yi kira ga gwamnati da ta qara wuraren shaqatawa da motsa jiki don qarin lafiya, domin kuwa ance rigakafi yafi magani.

Akwai abubuwa uku da ba su hudo kai har su addabi jama'ar wannan gari ba, sai bayan wajen shekaru hamsin (50). Na farko, akwai qyaqqyawan tsaro, jama'a kuma na bin doka. Saboda haka sace-sace da kashe-kashen jama'a abubuwa ne da suka shigo cikin garin saboda qarin jama'a da tavarvArewar tsaro. Na biyu, akwai zaman lafiya, lumana da sahalewar juna tsakanin mazauna wannan gari, waxanda suke da bambancin qabila da addini. Rikice-rikicen addini da qabilanci da ke varkewa su kuma kawo asarar rayuka da dukiyoyi sun shigo garin ne, a wannan zamani saboda tavarvArewar tattalin arziqin jama'a tare da rushewar tsarin mulkin adalci da hukuncin gaskiya. Na qarshe, shi ne isasshen abinci. A wannan zamani akwai yalwal abinci da kuma rahusa, akasarin mazauna garin ba manoma ba bane, ma'aikatan gwamnati ne saboda haka ana kawo masu hatsi daga garuruwan a Arewa. An kuma yi wa gwamnati jinjina saboda ba da magani kyauta a asibitocinta.

Babu shakka kamar yadda Sir Ahmadu yaci gaba da bunqasa shiri Gwamna Lugga mazauna wannan gari sun daxe suna zaman lumana da wadatar zuci.

---

[1] New Nigerian, (Editorial) Thursday, 5 Janurary, 1967, shafi na 6

Hasalima, duk gwamnoni da suka yi mulkin wannan gari qarawa da bunqasawar ayyukan da Lugga da Gwamji suka shimfixawa wannan garin Kaduna suke yi. Haka kuma tattalin arziqin qasa bai tavarvare ba saboda gwamnati na da qarfin ba da ilimi da kula da lafiyar jama'a dai-dai gwargwado.

Wannan gari ya ga mulkin Gwamnoni Turawa, da sojoji da farar Hula a lokuta daban-daban.

Gwamnonin Kaduna

Ranar 15 ga watan Janairun shekarar 1966, Nijeriya ta ga juyin mulki na farko, juyin mulkin da yake mummuna wanda kowane xan Nijeriya ba zai tava mantawa ba. A wannan juyin mulki ne manyan shugabanni suka kwanta dama, a cikin waxanda suka rasa rayukansu har da Firayim Ministan Nijeriya, Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa, da Firimiyan Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, da Firimiyan Jihar Yamma, Cif Akintola da sauran manyan shugabannin Qasar nan. Wannan juyin mulki shi ya kawo qarshen Siyasar Farko, ya kuma zama mabuxin shugabancin soja a wannan qasa. Wannan juyin mulkin ne kuma ya bai wa Manjo-Janar Aguiyi Ironsi ragamar shugabancin Nijeriya, shi ne sojan farko da ya riqe muqamin Shugaban Nijeriya.

Mulkin Ironsi bai daxe ba saboda an mayar masa da martani da aka yi a cikin wani juyin mulki da shi shugaba Ironsi xin ya rasa ransa a cikin watan Yuli na shekarar 1966. A wannan juyin mulki ne, Leftanar Kanar Yakubu Gowon (daga baya ya zama Janar), ya zama Shugaban Nijeriya kuma Kwamandan Sojoji. Wannan juyin mulki na biyu a tarihin Nijeriya, shi ya haifar da yaqin basasa, a lokacin da Leftana-Kanar Odumegwu Ojukwu ya valle, ya kuma nemi ya mayar da Jihar Gabas, qasa mai zaman kanta, wato "Biafra. " A dalilin wannan yankuri ne sai aka gwabzar da 'yan Tawaye domin a tabbatar da zaman Nijeriya qasa xaya har ya zuwa ranar 1 ga watan Janairu na shekarar 1970, lokacin da suka ba da kansu.

Shugaban Qasa, Janar Gowon ya yi shirye-shirye a farkon hawansa ragamar mulkin Nijeriya. Xaya daga cikin abin da ya yi, shi ne qirqiro Jihohi goma sha-biyu daga tsofaffin Jihohin Nijeriya uku a shekarar 1967. An raba Arewa zuwa Jihohi shida:- Jihar Arewa ta tsakiya, da Jihar Kano, da Jihar Arewa maso Yamma, da Jihar Arewa maso Gabas da Jihar Binuwai da Filato, da Jihar Kwara. Kowace Jiha tana da Gwamna.

Saboda rarraba Arewa da aka yi, sai tsohon gwamnan Arewa, Manjo Hassan Usman Katsina (Manjo-Janar daga bisani), ya zama shugaban wata Qungiya ta wucin gadi mai kula da tattalin arziqin Jihohin Arewa baki xaya, wato *Interim Common Service Agency* (ICSA), muqamin da ya riqe yana zaune a Gidan Gwamnati da ke Kaduna. Saboda haka sai gwamnan Jihar Arewa ta tsakiya, Birgediya Abba Kyari sai ya maida hedkwatar Jiharsa Zariyana wani xan lokaci.

Saboda zaman shugaban ICSA, a Kaduna. A Zariya ne gwamnan ya naxa kwamishinoninsa, amma daga baya ya dawo da hedkwatar Jihar Kaduna, inda ya zauna a Gidan Gwamnati. Saboda qirqiro jihohi da aka yi sai ya kawo qarshen aikin ICSA.

Kaduna ta samu ci gaba sosai lokacin wannan Gwamna. A lokacinsa ne aka qirqiro mulkin En'e a Kaduna a cikin shekarar 1972. A wannan shekarar ce, Birgediya Abba Kyari ya kafa harsashin mulkin sarauta ta gargajiya, domin an naxa Hakimai guda biyar da 'yan Majalisa a garin Kaduna. Alhaji Nuhu Bamalli shi ne aka naxa shugaba mai cikakken ikon mulki na En'e ta Kaduna. Wannan babban mataki ne na tabbatar da ganin Kaduna ta samu sarautar gargajiya wadda Zazzau ta amincewa.

Amma mulkin Gowon ya zo qarshe a watan Yuli na shekarar 1975, a wani juyin mulkin da ba a zubar da jini ba. A wannan juyin mulki ne, Janar Murtala Ramat Muhammad ya zama Shugaban Qasa kuma Babban Kwamandan Sojojin Nijeriya. A lokacin wannan jan gwarzo ne, aka qara jihohi shida suka koma jihohi 19 ke nan a Nijeriya. Ya kuma kawo tsarin Qananan Hukumomi don su maye gurbin na En'e. Wannan mataki ne na ganin an kusanta jama'a ga hukuma. gwamnan Kaduna na wannan lokaci shi ne Guruf Keftin Usman Jibrin.

Qaramar Hukumar Kaduna na da yankin mulki *Administrative Area* guda bakwai, qarqashin shugaban Qaramar Hukuma, wato *Local Government Chairman*. Wanda ya fara cin zaven shugaban Qaramar Hukumar Kaduna shi ne, Alhaji Yusuf Xantsoho daga shi kuma sai Alhaji Kabiru Umar daga nan sai Alhaji Sadau Usman.

Janar Murtala Muhammad ya rasa ransa ne a wani juyin mulkin da bai yi nasara ba, a ranar 13 ga watan Fabrairu na shekarar 1976, wannan ya bai wa Janar Obasanjo damar samun ragamar shugabancin Nijeriya. A lokacin mulkin Obasanjo ne, gwamnan Kaduna Usman Jibrin ya yi ritaya, sai Guruf Keftin Muktari Muhammad (1976-1977) ya zama gwamnan Jihar Kaduna.

Saboda shirye-shiryen miqa mulki ga farar hula da aka yi niyyar yi a shekarar 1979, sai aka naxa Kantomomi don su maye gurbin gwamnoni domin ba da mulki. Guruf Keftin Ibrahim Alfa (1977-1979) shi ya riqe wannan muqami a Jihar Kaduna.

Ranar 1 ga watan Oktoba na shekarar 1979, Janar Obasanjo ya damqa ragamar mulkin Qasar nan ga Alhaji Shehu Usman Shagari wanda ya zama Shugaban Qasa Mai Cikakken Iko. Wannan shi ya kawo mulkin Farar Hula a karo na Biyu. Wanda aka zava gwamnan Jihar Kaduna kuwa, shi ne Alhaji Abdulqadir Balarabe Musa (1979-1981). Amma wannan gwamnan sai 'yan Majalisarsa suka tsige shi a shekarar 1981, saboda haka sai mataimakinsa, Alhaji Abba Musa Rimi ya zama Gwamna har zuwa qarshen 1983. Sojoji sun sake yin juyin Mulki a

shekarar 1983. Alhaji Lawal Kaita (Oktoba 1983-Disamba 1983)shi ke gwamnan Kaduna kafin juyin Mulkin Soja, wanda ya hamvarar da mulkin Farar Hula.

Sojoji sun karve mulkin Shugaba Shehu Shagari a ranar 31 ga watan Disamba na shekarar 1983, a wannan juyin mulki ne Manjo-Janar Muhammadu Buhari ya zama Shugaban qasa. Wanda ya zama gwamnan Jihar Kaduna a wannan lokaci, shi ne *Air Commodore* Usman Mu'azu (1984-1985). Mulkin Buhari ya zo qarshe a ranar 27 ga watan Agusta na shekarar 1985. A wannan sabon juyin mulki ne sai Manjo-Janar Ibrahim Babangida ya hau ragamar mulkin qasar. Sai Leftana Kanar Abubakar D. Umar (1985-1988) ya zama gwamnan mulki soja. Sauran gwamnonin wannan jiha daga wancan lokaci zuwa yanzu su ne masu girma; Kanar Abdullahi Sarki Muktar (1988-1990), da Kanar Tanko Ayuba (1990-1991), Alhaji Dabo Mohammed Lere (1991-1993), da Kanar Lawal Jafaru Isa (1993-1996), da Kanar Hammed Ibrahim Ali (1996-1998), da Kanar Umar Faruk Ahmad (1998-1999). A wannan zamani Cif Olusegun Obasanjo ya zama shugaba, a qarqashin mulkin Farar Hula. Ya samu shekara takwas yana mulki, da Alhaji Ahmed Muhammad Maqarfi a matsayin Gwamna (1999-2007). Daga shi sai gwamnan da ke kan gadon mulki a yanzu, Arc. Muhammad Namadi Sambo, wanda ya kama mulki daga watan Mayu na shekarar 2007. A wannan lokaci Alhaji Umar Musa Yar'adua ke Shugaban Kasa. Shi ya qarbi ragamar mulki daga tsohon Shugaban Qasa Cif Olusegun Obasanjo. A duk waxannan zamanin Gwamnoni, Kaduna ne hedkwatar mulkin wannan jiha. A waxannan lokuta kuma garin ya samu qarin ci gaba daban-daban.

Rediyon Kaduna (NBS)

Yaqin Duniya na biyu yana xaya daga cikin a zabi xaya kafa gidajen rediyo a qasashen Yammacin Afirka. Kafin varkewar wannan yaqi akwai gidan rediyo xaya tak a duk faxin Yammacin Afirka. Wannan gidan rediyo na qasar Ankara ta qasar Ghana, yana kuma watsa labarai da shirye-shirye masu qayatarwa cikin Hausa.

Ma'aikatan sashen Hausa na farko, daga Arewacin Nijeriya ake kawo su domin gabatar da shirye-shirye cikin Hausa. Ma'aikatan na wannan lokaci su ne; Alhaji Isa Kaita Wazirin Katsina da Marigayi Malam Bello Xandago (Mai Dawakin Tuta). Daga bisani Dungus Maiduguri da Sani Kwantagora suka maye gurbinsu. Su waxannan ma'aikata sun taimaka qwarai wajen bunqasa Gidan Rediyon Ankara da shirye-shirye masu ban sha'awa.

Varkewar yaqin duniya na biyu a cikin shekarar 1939, ya janyo qara buxe tasoshin rediyo a Yammacin Afirka don wayar da kan jama'a tare da watsa furofagandar Yaqin Duniya ga jama'ar Nahiyar Afirka. A Nijeriya an fara buxe gidan rediyo a wani qaramin gidan Katako da ke "Ikoyi Crescent " a Ikko. Daga baya aka kafa wajen watsa ayyukan rediyon a bisa benen "Glover Memorial Hall

" na Ikko. A wannan lokaci da aka kafa Gidan Rediyo a Ikko a Arewacin Nijeriya ma a Zariya kuma an kafa jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo wadda Alhaji Abubakar Imam yake Edita don su taimaka wajen watsa labaran yaqin duniya na biyu (World War II).

Buqatar da take akwai ta buxe gidan rediyo a Arewa, ta tilasta horar da ma'aikata domin yin wannan aiki. Saboda a zavi nagartattun ma'aikata sai aka sanya gasar karatu ga xaliban tsohuwar kwalejin Katsina don samun wanda za a aika Ikko don ya sami horo don ya zama ma'aikacin rediyo wato, "Senior Wireless Monitor and Announcer. " Wanda ya yi zarra a cikin waxannan xalibai, shi ne wani gawurtaccen xalibi mai basira da rashin tsoro mai suna Raji Abdullahi. Shi mutumin garin Okene ne, shi ne kuma aka tura Ikko don yin kwas na aikin watsa labarai.

A wannan lokaci aka buxe gidajen rediyo a garuruwan Enugu da Ibadan da Kano wato dai kowace Jiha tana da gidan rediyo guda xaya tak ke nan. Gidan rediyon farko da aka buxe a Arewa shi ne na Bompai a birnin Kano a cikin shekarar 1944. Daga nan aka buxe wani a Zariya a shekarar 1945 da Jos da Kaduna ita ma dai a shekarar 1948.

Rediyon Bompai da ke Kano a wannan lokaci, yana watsa shirye-shirye daga gidan rediyon BBC na London, shirye-shiryen Hausa kuma daga Ankara ta qasar Ghana kafin shekarar 1945. Amma daga qarshen yaqin duniya na biyu, sai rediyon ya fara watsa ayyukansa saboda kafa hanyoyin watsa labarai wato "*Radio Diffusion System*.[1]

An kafa gidan rediyo a Kaduna a cikin shekarar 1948, a matsayin *Radio Diffusion System* qarqashin ma'aikatar "P&T " da ma'aikatar watsa labarai. An bunqasa gidan rediyon a ranar 1 ga watan Afrilu na shekarar 1951 lokacin da aka naxa daraktan shirye-shirye da mataima kansa.

A cikin shekarar 1952 gidan rediyon ya fara yin amfani da tiransimita mai qarfin 7½ kilowatt. Alhaji Abba Zoro shi ne ya fara watsa labarai ta wannan sabuwar tashar watsa shirye-shirye. A hankali rediyon yaci gaba da bunqasa, bayan shekaru biyar ya samu tiransimita mafi girma, inda ya zama *Nigerian Broadcasting Corporation*. A watan Maris na Shekarar 1954 ne gwamnatin Jihar Arewa ta havaka ayyukan gidan wannan rediyo da sabaon inji, wanda aka yi bikin buxe shi.

Shagalin Buxe Sabon Injin

A watan Maris xin shekarar 1954 aka yi babban taro a Nasarawa Unguwar a (yanzu) ta Kaduna can kusa da gidajen Ministocin Jihar Arewa, don bikin buxe babban injin na wayar iskar jiha. Wannan sabon injin ya fi na da qarfi sau ashirin.

---

[1] Hira da Alhaji Shuaibu Maqarfi a Fabrairu, 1985.

Kamfanin Marconi na Ingila su suka zayyana shi, kuma suka yi shi. Lokacin da aka gama shi, aka jarraba shi na tsawon wata shida a xakin kimiyya, sa'an nan aka xauko shi cikin jirgin sama zuwa nan Kaduna. Kamfanin Marconi su ne kuma suka haxa shi a nan Kaduna tare da waxansu injiniyoyi na ma'aikatar rediyon Nijeriya.

A wajen wannan taro akwai Turawa da Baqar Fata da Sarakuna duka. Mr. Wilkinson shi ya sadad da Mr. T. W. Chalmers, direktan ma'aikatar rediyon Nijeriya, wanda ya zo takanas don wannan shagali. A cikin jawabinsa na buxe wannan injin har ya ce, "Ya Mai girma, ya Mai girma minista, ya jama'ar da ke nan duka, mata da maza. Yau ranar babban farin ciki ce gare ni da dukkan masu aikin rediyo na Nijeriya. Babban abin alfarma ne gare mu mu yi muku maraba a nan da kuka baqunce mu. Shekaru uku da suka shige, babu ma'aikatar rediyo a Nijeriya. A lokacin nan sai mutum biyu kaxai, Mr. Murray da ni kaina. A lokacin muna nan Arewa muna yin shirye-shirye. Wannan abin da kuka gani a yau shi ne xaya daga cikin amfanin da a ke girba na shirye-shiryen nan. "[1]

Yaci gaba da cewa mutane qalilan ne ke da akwatunan rediyo, ko da yake dai yawan masu akwatunan yanzu ya ninka na bara biyu. Ma'aikatar rediyon Nijeriya tana taqama da aikinta na ba da labarai da taxuxxuka. Sha'anin labarai yana hannun wanda ke a da shi ne Editor na Citizen, Mr. England. Tushen samun labari da ilimi yana wurin rediyo, don haka zai zamo al'amari mafi girma wajen samun mulkin kai. Wayar Iskar Ingila ta ba da aron ma'aikatanta 16 ga ma'aikatar rediyon Nijeriya. Ya ce, "Cikin 'yam mako kaxan zan koma BBC, wani zai maye gurbina. Shekaru ukun da na yi a Nijeriya sun sa ni babbar qaunar qasar Nijeriya da mutanenta. " Ya qarasa jawabinsa da murna da godiya ga dukkan waxanda suka taimaka wajen kafa wannan injin.

Daga nan kuma Ministan Mulkin En'e da Kyautata zaman jama'a, Mai girma Sardaunan Sakkwato Malam Ahmadu Bello ya yi nasa jawabi. A ciki ya ce, "Na yi farin ciki da Allah Ya kawo mu wannan rana ta yau da zan yi magana da ku duka ta wannan babban injin mai baza labaru wanda Arewa ta samu. Wani abin sha'awa, shi ne wannan injin an kafa shi kusa da gidana a nan Kaduna. Wannan sabon injin mai baza labaru ya fi ko wanne da aka tava samu a Arewa. Kuma na fahimci cewa jarabawar da aka riqa yi da shi kamar wata guda, ta nuna ingancinsa, domin labarun da a ke bayarwa daga nan Kaduna ana jinsu har Saliyo da Golkwas, kuma ko ina a Jihar Arewa.

Yaci gaba da cewa, "Ina son in ga a kowane qauye komai qanqantarsa an sami a qalla akwatin rediyo guda da kuma akwatuna masu yawa a manyan qauyuka. Ta hanyar waxannan akwatunan rediyo kuna iya jin abubuwan da aka shirya muku don nishaxi da kuma qara iliminku na yadda duniya take tafe. "

---

[1] GTK 3 ga Maris, 1954, shafi na 7

Ya ce, "Idan Arewa tana buqatar mulkin kai ba da jin ba, to, tilas ne ku fahimci abubuwan da a ke yi, kuma ku shirya ga sanyanaku taimako a cikin abubuwan da gwamnatin jiha ke aikatawa. Yadda za ku yi taimakon shi ne ku san abin da a ke ciki, kuma ku zavi na gari lokacin da a ke zaven wakilanku a cikin majalisun garuruwanku da Majalisar Jiha da kuma Majalisar Tarayya. "[1]

Daga nan Sardauna ya yanke wani kirtani, ya buxe wannan wuri. Mutane suka xunguma, zuwa kallon wannan wuri. An rufe taro da qarfe shida na Yamma, bayan an yi xan lashe-lashe.

A shekarar 1957, wannan gidan rediyo ya samu ma'aikata waxanda suka maye gurbin baqi Turawa Babban shugaban wannan gidan rediyo na farko, shi ne Mista J. F. Wilkinson da mataimakinsa Alhaji Muhammadu Ladan xan lyan Zazzau wanda shi ne ya zama xan Arewa na farko da ya shugabanci wannan gidan rediyo. Sauran tsofaffin ma'aikatan su ne, Alhaji Shu'aibu Maqarfi mai watsa labarai, da Bello Jisambo shugaban ma'aikata da Mista Dolli shugaban vangaren labarai. Sauran shugabannin gidan rediyon su ne, Alhaji Sani Kwantagora, da Alhaji Abubakar El-Nafaty da Mista J.H. Chindo da Misis Hamman. Dukkansu sun taimaka matuqa wajen bunqasa gidan rediyon.[2]

Ma'aikata masu yawa sun taimaka wajen bunqasar gidan rediyon. Wajen waqe-waqe kuwa, akwai kamar su Alhaji Mamman Shata Katsina a kan sanya faya-fayensa a kowace ranar Alhamis. A lokacin farko tashen waqarsa ne, kuma a kowace ranar sa ne Jama'a su kan yi cincirindo su kewaye akwatin rediyo suna sauraren kixe-kixensa. Haka kuma sauran makixa kamar su Salihu Jankixi da Sarkin Taushin Katsina da Musa Xanqwairo da Garba Maitandu da Hamisu Sarkin Kixa da Ibrahim Narambixa da sauransu duk sun taimaka wajen bunqasa gidan rediyo a Nijeriya.

Wajen Fannin Addini kuma, rediyon ya taimaka qwarai da gaske wajen fahimtar da jama'a Addininsu. Malam Isma'ila da Malam Mamman Kano su ke wa'azin musulunci da Alhaji Ibrahim Arab shi ne kuma yake karatu daga cikin Alqur'ani Mai girma. Akwai kuma rabin sa'ar Kirista saboda Kirista waxanda ake yin wa'azin nasu a kowace ranar lahadi.

Shirin masu sauraronmu ya taimaka wajen kusantar da jama'a ga shugabanninsu. A wannan shiri ne jama'a ke rubuto wasiqu suna yi masu godiya ko kuma roqon hukumarsu da ta taimakesu da abubuwan jin daxi. Zamanin nan namu, shirin da Alhaji Shu'aibu Maqarfi ke yi, ya taimaka wajen tariyar jama'a da koya masu zaman duniya. Kusan kowa ya san filin Jatau Na Albarkawa wanda Alhaji Ango Zariya yake gabatarwa, ba qaramar taimakawa ya yi ba wajen

---

[1] GTK 3 ga Maris, 1954, shafi na 7

[2] Hira da Alhaji Shuaibu Maqarfi a Fabrairu, 1985.

bunqasa rediyo a Arewacin wannan qasa. Malam Mamman Kano da shirinsa na Dare Dubu da xaya da wa'azin musulunci sun qayatar qwarai da gaske.

A lokacin da ayyukan gidan rediyo ya kankama sosai, sai buqatar kafa gidan rediyo mai hoto wato talbijin ta taso gadan-gadan. A wannan lokaci kuma gwamnatin Jihar Arewa ta samar da da tashar talbijin a wannan hedkwata.

Tashar Talbijin

A ranar sha biyar ga watan Maris na shekarar 1962 ne aka qaddamar da matakin farko na fara sarrafa sabuwar tashar Talbijin a babban birnin Jihar Arewa, Kaduna. A lokacin ne kuma aka qaddamar da wata tashar rediyo mai qaramin zango da zai gauraye dukkan faxin Jihar Arewa da amo. A watan Afrilun wannan shekarar ne kuma ake sa ran cewa faxaxa aikin tashar da ake yi zai kai Zariya da Kano don kallon shirye-shiryen talbijin da kuma sauraron sabon rediyon da aka yi wa laqabi Rediyon Talbijin Kaduna.

Firimiyar Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello ne ya furta haka yayin da ya kai ziyarar aiki ta awa biyu don dudduba ofisoshi da kuma xakunan xaukar shirye-shirye na talbijin da rediyo, waxanda ake ta qoqarin kammala aikin ginawa.

Babban Sakataren ma'aikatar yaxa labarai ta gwamnatin Jihar Arewa, Mr. W.D. Wilson ya fayya cewa Firimiya cewa kafin qarshen shekarar za a maye makwafin tsohuwar na'urar watsa shirye-shirye mai gajeren zango da wata mai matsakaicin zango da ke da qarfin kilowatt 250, wacce za ta kasance babu kamarta a qasashen Afrika da ke Kudu da Sahara. Qara qarfin tashar zai jawo hankalin masu talan hajojo da sana'o'insu a tashar.

Daga cikin wuraren da Firimiya ya ziyarta har da babban tashar yaxa shirye-shirye a Jaji, wacce da ke nisan mil ashirin da huxu kan babban hanyar Kaduna zuwa Zariya, da kuma inda wurin wucin gadi da aka samar da xakunan shirye-shirye a Makarantar Koyon Fasaha, da ke kusa da Kwalejin gwamnati na Kaduna, da kuma gidajen manyan ma'aikatan tashar da ke kan titin Dawaki, kusa da sansanin Dawakan Daba wato Murtala Square da kuma wurin da aka yi niyyar gina wuraren dindindin na xaukar shirye-shiryen talbijin da na rediyo, da kuma ofisoshin gudanar da harkokin mulki da ke kan *Hosptal Road*, (yanzu Yakubu Gowon Way). An tabbatarwa Firimiya Sir Ahmadu Bello cewa duka-duka kuxin da ayyukan za su ci idan an kammala aikinsu ba zai wuce Fam dubu xari ba.

A tashar yaxa shirye-shirye ta Jaji, babban sakataren ma'aikatar yaxa labarai, Mr. D.W. Wilson ne ya karve shi, sa'anan kuma ya gabatar masa da Mr. R.D. Horner, babban maginin ofisoshi da sauran wuraren gudanar da aikin tashar talbijin xin. Shi dai Mr. Horner wani jami'i ne daga kamfanin mashahuran magina na Farfesa Corfoialo na Jami'ar London, kumafitacce, kana kuma qwararre a fannin zayyana gine-ginen da za su dace da al'adun musulunci. Daga nan kuma sai

ya qara gabatarwa Firimiya da Mr. Leslie Diamond, manajin Darakta na farko na kamfanin yaxa balabarai na gwamnatin Jihar Arewa, wato *Broadcasting Company of Northern Nigeria*, (BCNN) da kuma Mr. J. R. Romanies, babban injiniyan kakkafa nau'urorin sadarwa daga kamfanin xaukar sauti a fayafayan garmaho, wato EMI, da kuma wakilan wani kamfanin sayar da na'urorin sauti da na kallon hotuna na General Contracting Company waxanda ke aiwatar da aikin kwangilar gina kamfanin.

Sa'ilin da yake zagaya da Sir Ahmadu Bello wurare daban-daban na tashar, babban maginin ya ce za a kammala aikin a qarshen watannan, kuma kafin ranar sha biyar ga watan Maris dukkan na'urorin da ya kamata a samar an gama kakkafa su. Ya kuma qara da cewa babban matsalar da suka fara samu shi ne na qurar da ta shisshige cikin gine-ginen, amma sai dai an rigaya an xauki matakan hana sake afkuwar haka nan gaba. Ya kuma nunawa Firimiya taswirar ginin kamfanin. Shi kuma Sir Ahmadu Bello ya mayar da jawabi, yana mai cewa, fatanmu shi ne samun tashar talbijin da na rediyo da ba irinta a qasar, ko kuma a nahiyar Afrika.

A wuraren da aka gina xakunan tsara shirye-shirye a Independence Hall, na Makarantar Koyon Sana'o'i da ke harabar Kwalejin gwamnati ta Kaduna, Mr Diamond, Manajin Daraktan kamfanin BCNN ne ya zagaya da Sir Ahmadu Bello, har ya ga wata na'urar yaxa shirye-shirye mai qarfin watt xari wacce aka daxe da kafawa. Shi kuma babban maginin, Mr. Horner ya faxawa Sir Ahmadu Bello cewa an tanadi ton arba'in na busasshiyar qasa don yin anfani da su a xakunan wucin gadi na tsara shirye-shirye-shirye ta yadda za su hana wani sauti daga waje shigowa idan ana xaukar shirye-shiryen.

A can kusa da sansanin dawakan daba, wato Dawaki Road, an zagaya da Sir Ahmadu Bello xaya daga cikin gidajen manyan ma'aikatan kamfanin waxanda aka ce ba kamansu a duk faxin garin Kaduna wajen zayyana da kuma gini mai ban sha'awa, irin na zamani. A can wurin da aka tanada don samar da ofisoshin kamfanin na dindindin kan *Hospital Road* (Yakubu Gowon Way a yanzu), inda a halin yanzu ake rurusa gidajen da ke wurin don yin gini, an faxawa Sir Ahmadu Bello cewa za a kammala aikinsu a qarshen watan Oktoba, kuma kafin qarshen watan Disamba za a kammala kakkafa dukkan na'urorin da ake buqata don tashar ta fara aikin gadan-gadan.

A qarshen ziyarce-ziyarcen, Sir, Ahmadu Bello ya ce ya gamsu da dukkan abubuwan da ya ganinma idanunsa, ya kuma qara da cewa ya tabata cewa wannan kamfani na BCNN zai burge kowa da kowa yayin da aka fara gabatar da shirye-shiryen rediyo da na talbijin. Daga nan sai ya yabawa Ministan yaxa labarai, Alhaji Ibrahim Biu, wanda ya rufa masa baya yayin ziyarce-ziyarcen, duk kuwa da cewa akwai wasu muhimman ayyuka a gabansa.

Daga cikin waxanda kuma suka raka Sir Ahmadu Bello akwai Ministan Ilimi, Alhaji Isa Kaita Madawakin Katsina, da Alhaji Muhammadu Bashar, Wamban Daura da kuma Ministan Tsimi da Tanadi.[1]

Gidan Shawara

Gidan Shawara, wato "*Lugard Hall*, " an gina shi ne domin tunawa da Gwamna Lugga. An yi wannan gini ne a inda gwamnan ya zava da kansa da a yi gidan Gwamna Janar na Nijeriya, inda burinsa na mayar da Kaduna hedkwatar Nijeriya yacika. To, da yake ba a cimma wannan manufa ba, sai aka gina gidan shawara a wurin da sunan qwararren soja kuma masanin mulki wato Gwamna Lugga.

Waxanda suka aza harsashin wannan gini su ne, gwamnan Nijeriya da, Alhaji Sir Abubakar na uku, a cikin watan Mayu na shekarar 1947. Maqasudin yin wannan gini, shi ne don 'yan Majalisu su riqa yin taro a ciki. An sha wuya kafin a kawo kwanon rufin ginin, tun ma ba lanqwasassun nan ba da aka yi rufin tulluwan nan da su, haka ginin yake a buxe ga shi ga sama'u.

Kafin a gama ginin Gidan Shawarwari, duk taron da za a yi a makarantar sana'a ake yi, wato gine-ginen da ake amfani da su wajen koyar da ilimin fasaha waxanda ke Yamma da tashar jirgi ta Doka (Kwalejin gwamnati a yanzu), wannan shi ne ginin da ke akwai a Kaduna, Ko da yake bai cika dacewa ba, tsawo gare shi kuma bai da faxi, 'yan kallo kuma sai a dunqule su wuri xaya kamar shanu inda ba su jin abin da ake cewa balle su gani. Kafin a gama wannan gini, 'yan Majalisar Zartarwa, a farkon kafa ta, a xakin cin abinci suka yi taronsu na farko. Sardauna wanda yake yana xaya daga cikin 'yan wannan Majalisa ya ce:

"Muka yi taro a xakin cin abinci na Gidan Gwamna a Kaduna, wurin da yake ko kaxan bai dace da a yi taron kan al'amuran asiri na Jihar a wurin ba. Boyi-boyi na ta kai da komawa, daf da wurin da ake taron, sa'an nan kuma ga wata qofa voyayya da ta shiga xakin da a ke tara abinci kafin a fara ci. "[2]

Har ila yau an yi fama da qarancin wajen taro, sai kuma ga shi an sami qarin 'yan Majalisar Wakilai, amma gaggauta gama wannan gini cikin hanzari ya taimaka sosai. A dalilin haka ne ma Sardauna ya ce:

> *Babbar sa'ar da aka yi, ita ce ana dai-dai gama ginin gidan shawara na Kaduna ke nan, don a sami karvar sabbin 'yan Majalisar Wakilai. Wannan ma sai mu ce faxuwa ta zo dai-dai zama ke nan, domin in ba domin samun wannan ginin ba, da sai muzama ba mu da*

---

1 *The Nigerian Citizen Asabar*, 10 ga Maris 1962.

2 Ahmadu Bello, *Rayuta*, shafi na 90

wurin yin shawara ke nan. Mun ma riga mun yi taro xaya ko biyu a ciki na tsohuwar Majalisar da aka rushe. A lokacin kuwa ko daven ma ba a yi ba, ba wurin zama, ina tsammani ma ko rufi ba a gama ba. Muka dai shiga Haka nan, saboda girman ginin, sai muka zama kamar kwabo xaya a aljihu. Kuma irin kayan aikin nan na qara xaga murya, ba su cika aminci sosai ba, abin dai gwanin ban haushi, har ma muka riqa tunanin cewa shin anya kuwa ginin nan ana da niyyar qarasa shi dai? Sai ga shi an gama dai-dai lokacin da sabuwar Majalisa za ta yi taro. Wannan al'amari yana ba mu mamaki, ainun, yana kuma qayatar da baqi, waxanda suka zo daga qasashen qetare.

Don ma ka ji, ka qara al'ajabi, shi wannan Gidan Shawara na farko, an yi shi ne don ya ishi Wakilai tamanin kurum, wato bisa ga buqatar da ake da ita a wannan lokaci, an riva yawan ginin sau biyu ke nan. Ganin haka shi ya sa aka zaci an kange yadda wata rana za a ce ana son qara wani ginin. Kafin dai a gama ginin sarai, yawan Wakilai sun kai 105, a qarshe ma sai ga shi ana cunkusa mutane 150 a ciki. Lokacin da aka gama Sabon ginin da a ke yi, sai Wakilai su riqa nasu taron a can, wannan tsohon kuma zai dace da yawan Sarakuna.[1]

An gama ginin gidan shawarwari a shekarar 1951, an kashe kuxi fam xubu hamsin da takwas (£58,000) wajen gama shi. Irin wannan gine-gine da aka yi an bi salon gine-ginen Musulmin Arewacin Afirka da na Gabas ta tsakiya ne. An qara faxaxa ginin da sabon xakin 'yan majalisu wanda gwamnan Arewa, Sir Gawain Bell ya buxe a ranar 13 ga watan Maris ta shekarar 1962.

Majalisar Garin Kaduna

An yi shekaru da dama maganar yadda za a mallaki Kaduna tana bai wa Turawan Ingilishi wahala a zukatansu. Sir Ahmadu Bello ya fahimci wannan matsalar sosai da sosai don haka ne ma ya ce: "Gwamna Lugga an koya masa aikin soja, kuma goguwa ta yau da kullum ta sa ya zama qwararren soja, don haka a ko yaushe tunanin abubuwa irin waxannan suna cikin zuciya tasa kuma shi gwanin iya mulki ne, don haka ya san muhimmancin samun hedkwata wadda ta dace don a ji daxin tafiyar da mulki. Ko da yake Dungurun ita ce ya fi so da can da farko, amma daga baya sai ya ga ba ta dace da abubuwan da aka zave ta dominsu ba. Zariya ko Kano su ne kuma ya kyautu a duba a gani ko za su dace. Dukkansu dai hanyoyi sun wadacesu, suna kuma da yanayin qasa mai kyau, wato a bisa ganin Bature, Zariya ita ce ta fi dacewa:

[1] Ahmadu Bello, *Rayuta*, shafi na 93

"Amma Lugga sai ya ga ai kuskure ne a kafa hedkwatar gwamnati a garin da wani Sarkin yanka yake. Irin duk yadda gwamnati ta kai ga ba da bayani, wannan ba zai hana Sarkin jin cewa ya fi sauran Sarakuna daraja ba, wato ya kaucewa tsarin darajar Sarakuna ta da, don saboda damar da ya samu don zuwan baqi da suka zo da nasu sabon mulkin. Kuma bisa gaskiya shi ma Sarkin ba zai so a kafa masa hedkwatar gwamnati a garinsa ba, domin sai ya rasa sukuni, tun ba ma idan ya ga gidan gwamnati ya fi nasa kwarjini ba. Da Jos ya kamata a tuna da ita amma a lokacin nan hankali bai kwanta ba, don haka ba a cika ambatonta ba. "[1]

Matsayin Kaduna hedkwatar Arewa ya haifar da matsololin mulkin garin a lokuta daban-daban. An xauki matakan inganta mulkin garin Kaduna, a ciki harda kafa Majalisar Garin Kaduna.

A cikin watan Mayu na shekarar 1954 jama'ar da ke zaune a Kaduna ta taka wani tsani a gaba na tafiyar da al'amarun yau da kullum, waxanda suka shafi zamansu na duniya. A ranar Asabar, 1 ga watan, Mayu, En'e ta Zariya ta kafa Majalisar Garin Kaduna. Wannan majalisa ce za ta xauki dukkan ayyukan ciyar da garin Kaduna, Sabon Gari da Tudun-Wadan Kaduna gaba. Za a miqa mata wani ikon tafiyar da mulkin wurin da kuma amanar kashe waxansu kuxaxe. Zaven masu shiga Majalisar za a yi shi ta hanyar qabilu ne. Di'on Zariya Mr. J.C.H. Farmer, ne ya bayyana wannan sabon tsarin mulki sa'ad da aka yi taron qabilu a xakin taruwa na Kaduna.

Wato xaya ga Mayu, ita ce qarshen rayuwar hukumar da ke ba da shawara, wato *Town Council* wadda a ke da ita tun tuni a Kaduna. Wannan sabuwar Majalisa an kafa ta kusan bisa duk qa'idodin da aka bayyana a cikin rahoton kwamitin da Majalisar Zartarwa ta naxa domin ta duba maganar yadda za a tafiyar da mulkin garuruwa irin su Kaduna nan gaba.

An sami wakilai talatin da biyar cikin sabuwar Majalisar Garin Kaduna, M. Sambo Magajin Garin Kaduna kuwa shi ne shugaban majalisar. Masu shawara su ne za su zavi mataimakin shugaba daga cikinsu. Ga yadda aka zavo wakilan.

Ibo za su sami wakilai shida, Hausawa da Fulani biyar, Yarbawa uku, Nufawa biyu, 'yan Kamaru ta Kudu mutum xaya. Ijaw xaya, Benin xaya, Barebari xaya. Effik da Ibibio za su sami biyu, Itse da Urhobo xaya. Tiv xaya, Igala, Igbirra da sauran qabilun Arewa za a ba su wakili xaya. Waxanda ba 'yan Nijeriya ba za su sami wakili xaya.

Masu Unguwanni su huxu, za su shiga wannan Majalisa saboda matsayinsu na sarauta. Har ila yau kuma En'e za ta zavi mutane huxu waxanda za su wakilci waxansu abubuwa da aka ga ba a wakilta ba sosai a majalisar.

---

[1] Ahmadu Bello, *Rayuta*, shafi na 93

Shugabannin qabilu su ne, bayan sun yi taro sun zava, za su bai wa Magajin Garin Kaduna sunayen wakilan. A wannan taro ne Mr. Farmer ya roqi dukkan jama'ar Kaduna su manta da maganar zamansu qabilu daban-daban, su haxa kai su yi aiki tare yadda wannan majalisa za ta yi nasara, har mazauna Kaduna su ji daxi. Ya faxi a fili, cewa wakilci a majalisar ko kusa ba a so ya zama ta hanyoyin jam'iyyoyin mulki.

Sa'an nan Mr. Farmar yaci gaba da bayyana irin ayyukan wannan Majalisa. A ciki har ya ce majalisar za ta bai wa En'e shawara, za ta shirya istimat kowace shekara na irin buqatunta. Ya ce ba za a tsoma wa wannan Majalisa baki ba qwarai, sai idan En'e ta ga tilas ne ta yi haka, da niyyar gyarawa bisa hanyar mulkin En'e sosai.

Ya qara da cewa ce En'e za ta xebi wani abu cikin kuxin harajin da za a samu daga Kaduna, saboda tafiyar da ayyukan da har yanzu za su zama a hannunta. Im ba haka ba sauran duk kuxin da aka samu za a kashe su a Sabon Gari da Tudun-Wadan Kaduna ne.

An keve fam xari biyar (£500) don sanya kwalta a hanyan nan da a ke kira *Market Road*. An kuma keve jaka saba'in da biyar don gyaran hanyoyi. Haka kuma cikin shirin da En'e ta yi na shekara biyar ta keve fam dubu biyu da xari shida da goma sha-takwas (£2,618) don kyautata Kaduna.

Mr. Farmer ya faxa a wannan taro, cewa idan majalisar tana son ta qara samun waxansu kuxaxe, misali, tana iya qara kuxin lasin na su karnuka da na kekuna, ko kuxin kasuwa da sauransu. Mr. Farmer ya ce akwai duk waxannan dokoki, En'e ta kafa su da yardar Leftana Gwamna, in kuwa ana son canja su, tilas sai an canja dokokin.[1]

Sabuwar Majalisar Garin Kaduna ta yi taronta na farko. Irin wannan majalisa, ita ce ta farko da aka fara buxewa a lardin Zazzau. A cikinta akwai wakilai talatin da biyar da aka zavo su daga cikin kowace irin qabila da su ke zaune a Kaduna. A lokacin wannan taro, Magajin Garin Kaduna M. Sambo ne ya shugabanci taron. Di'on Zariya, Mr. J.C.H Farmer, da Kantoman Kaduna, Mr. S. McCallum sun halarci wannan taro.

M. Sambo ne ya karanta saqon da Sarkin Zazzau M. Jafaru ya aiko na kyakkyawan fatan alheri ga wannan majalisa. Shi kuma shugaban taron kuma Magajiin Garin Kaduna a cikin jawabinsa ya roqi Wakilai da cewa Ko da yake an zavo su ne ta qabilu, amma ya kamata su manta da cewa wane xan qabila kaza ne. Su haxa kai, baki xaya, su yi aiki don taimakon jama'ar da ke zaune a Kaduna duka.

Di'o Mr. Farmer ya yi nasa jawabi. A ciki har ya ce mafarkin da yake yi na kafa Majalisar Garin Kaduna tun tuni, to, ga shi dai ya tabbata. A nan ne kuma ya

---

[1] GTK, 21 ga Afrilu, 1954,

bayyana irin qoqarin da waxansu ma'aikatan En'e da na gwamnati suka yi, don a kafa wannan majalisa. Ya ce irin waxannan mutane za su yi murna qwarai, kuma suna fata wannan shiri da suka yi ya yi nasara.

Har wa yau kuma a cikin wannan taro ne aka zavi M. Bala Kafi ya zama shi ne mataimakin shugaba. M. Aliyu Adama Bida kuwa shi Wakilai suka zava ya shiga cikin kwamitin da ta ke lura da kyautata sha'anin ilimi a Kaduna. An kuma zavi Wakilai biyar, su ne za su lura da sha'anin kuxi wato kwamitin kuxi.

Ita wannan majalisa zata riqa baiwa En'e shawara akan dukan abubuwan da za su taimaka wajen ciyar da Kaduna gaba. Ita kuma ce za ta xauki alhakkin kyautata jin daxin zamansu.[1] A dalilin haka aka kafa kwamitoli iri-iri don cimma manufofin wannan majalisa.

Wajen yawan mutane kuma, kullum Kaduna sai qaruwa take yi. Cikin shekarar 1939, akwai mutane xubu huxu da xari uku da talatin da shida (4,336) a Kaduna, cikin 1960 kuma yawansu ya kai xubu sabain da uku da xari uku da arba'in da shida (73,346). Tsawon Kaduna kamar mil goma sha-xaya ne daga Gabas zuwa Yamma. Wurin har yanzu qaruwa yake yi, ga alama kuwa za ta ci gaba da qaruwa.

Har zuwa shekarar 1956, harabar Kaduna duk qarqashin lardin Zazzau take, En'e ta Zariya har tana ma da xan Ofishi a wurin, ma'aikatan Sarki a qarqashin shugaban su guda, su ne suke tafiyar da komai da komai. Wannan yana qarqashin ikon Razdan na Zariya ne wanda ya kan ma zo rangadi ya xan shaqata a nan. Ko ta yaya kuma Leftana Gwamna ba zai rasa sa bakinsa cikin harkokin garin nan da ke dab da shi ba, musamman ma kuma game da tabbatar da zaman lafiya, abu ne kuwa wanda yake mai rikitarwa, wani lokaci kuma abu ne wanda ya shafi Sakataren mulki da Ofishinsa. Waxanda ba su cewa uffan, sai Ministoci waxanda yake hedkwatarsu ce kuwa.[2]

A zamanin Firimiya sai aka dai-daita shawarwari kafa Yankin Qasar Hedkwata, wanda zai haxa da duk wuraren da aka riga aka yi gine-gine da kuma muhimmin filin jirgin saman nan: Wato za a vulgucewannan ne daga lardin Zazzau a sanya shi qarqashin ikon wani Minista (Sardaunan Sakkwato shi ne ya riqi wannan muqami). Mai tafiyar da mulkin wannan yankin qasar hedkwatar, zai kasancewani babban ma'aikacin gwamnati ko En'e-En'e. Wurin da ma dai can 'yan Sanda ke duba shi, musamman wajen da gine-ginen gwamnati suke cikin Gari kuma 'yan Doka.

Tun da babu 'yan Doka sai 'yan Sanda a yanzu, waxanda kasancewar ta su qarqashin gwamnatin Tarayya ne, zai janye wahala zuwa gaba, zai sami wata hukuma mai ba shi shawara, ba kuwa hukuma xaya, ba, amma hukumomin ba su

---

[1] GTK, 2, 2/6/1954

[2] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 212

da ikon zartar da komai sai su ba da shawara kullum. A nan an yi koyi ne da yadda ake yi a waxansu alqaryu na qasashen Ingila da Amirka kamar su Canberra da Washington, amma ba a zurfafa al'amarin yadda su suka zurfafa nasu ba, domin kuwa a can mazauna wurin ba su da 'yancin yin komai a matse suke.

Mulkin Kaduna tun kafin shekarar 1940, yana qarqashin "Administrator, " wato Kantoma, muqamin da Turawa ke riqe da shi. Cikin waxannan kantomomin Ingilishi, akwai Mista McCullum daga shi ne sai Mista Adam ya riqe muqaddashin Kantoma. A zamanin shi Mista Adam, ya gina babban ofishi a wurin da ofishin Magajin Gari Sambo yake a Unguwar da ake kira Unguwar Jaki. Saboda gina Babban Ofishin Kantoma a wannan waje, shi ya sa ake kiransa da ofishin Magajin-Gari. Daga baya muqamin Kantomanci ya dawo hannun 'yan qasa.

An sami sauye-sauyen mulki a cikin shekarar 1974, a lokacin gwamnan Jihar Kaduna ta tsakiya, Birgediya Abba Kyari ya qara wa Sarakuna Hakimai, da Dagatai qarfi ya kuma bunqasa mulkinsu. Kantoma kuma aka maye gurbinsa da muqamin Sakatare. Saboda qafa Qananan Hukumomi na Kaduna a shekarar 1976. Sakataren Qananan Hukumomin Kaduna na farko shi ne Alhaji Balarabe Mahmud daga shi waxanda suka riqe wannan muqami su ne, Alhaji Abdullahi Abubakar da Alhaji Jinaidu Yahaya da Mr. Musa Yohanna da Alhaji Ahmed Xalhatu. Shugaban qananan hukumomi na Kaduna wanda aka zava shi ne Alhaji Yusuf Xantsoho.

Amma Sarakunan gargajiya da shugaban qananan hukumomi na Kaduna da Sakatarorin dukkansu suna qarqashin Babban Shugaba. Alhaji Nuhu Bamalli Magajin Garin Zazzau. Wannan babban shugaba shi ne ya bai wa Hakiman garin Kaduna biyar muqamin gargajiya. Hakiman suna qarqashin shugabancin Alhaji Zakari Isa wanda Magajin Garin Zazzau ya bai wa muqamin "Sarkin Yaqi. " Shi ne Babban shugaba na garin Kaduna da kewaye baki xaya.

Hakimin Doka, Alhaji Garba an naxa shi muqamin "Wakili, " Hakimin Kawo, Alhaji Hassan shi ne da muqamin "Makama' da Hakimin Tudun-Wada, Alhaji Bawa Hayatu, mai muqamin 'Iya' da Hakimin Gabasawa Alhaji Sa'idu Labo mai mulkamin "Sarkin Gabas " da Hakimin Maqera, Alhaji Muhammadu Sani a matsayin 'Galadima'.

Kuma kowane Hakimi na da masu Unguwanni qarqashinsa. Doka akwai masu Unguwanni biyar da Tudun-Wada na da masu Unguwanni biyar da Kawo da Maqera da Gabasawa na da masu Unguwanni huxu-huxu.

Waxannan tsofaffin Hakimai sun sami sauye-sauyen muqamai saboda qirqiro Qaramar Hukuma da bunqasar garin cikin hanzari. A dalilin haka ne Sarkin Zazzau Alhjai (Dr.) Shehu Idris, CFR ya aka qara faxaxa mulkin gargajiya, aka kuma kara Hakimai da Dagatai. Sunan muqaman hakiman Qaramar Hukumar Kaduna Ta Kudu sai suka koma kamar haka:

Sunan Sarauta	**Masaurata**
Madaucin Arewa	Hakimin Barnawa
Barden Kudu	Hakimin Kakuri
Barayan Yamma Zazzau	Hakimin Maqera
Zannan Zazzau	Hakimin Tudun-Wada
Kachallan Zazzau	Hakimin Kurmin Mashi
Qwar Maza	Hakimin Unguwar Mu'azu

Masarautun Qaramar Hukumar Kaduna Ta Arewa

Bunun Zazzau	Hakimin Doka
Xankaden Zazzau	Hakimin Gabasawa
Xan Makwayon Zazzau	Hakimin Kawo
Falakin Zazzau	Hakimin Unguwar Shanu
Dokan Zazzau	Hakimin Malali
Xan Iyan Zazzau	Hakimin Kabala

Gidan masarautun garin Kaduna na qarqashin masarautar Zazzau ne. Ana kuma tafiyar da su ta yada ba za a kaucewa alqawarin da aka yi da Sarkin Zazzau Jafaru ba. Ranar 25 ga Yunin shakarar 1954 Leftana Gwamna Sir Bryan Sheawood Smith ya tattauna da Sarkin Zazzau Jafaru. A wannan lokaci ne Sarkin ya shaida wa Gwamna cewa: "Shi da jama'arsa za su yi naam da kafa wata qungiya domin shugabancin Kaduna, amma yana so a tabbatar masa cewa babu wani mutumin da za a naxa Sarkin Kaduna. "[1] Ya qara da cewa: Yin Sarki a Kaduna mai yiwuwa da sandar Sarauta wani abu ne wanda shi kansa da majalisarsa tare da jama'arsa ba za su amince ba! " Ko da aka bulguce garin Kaduna daga kaikashin Zariya a shekarar 1956 an yi la'akari da wannan gargaxi na Sarkin Zazzau.

Bunqasar Garin Kaduna

Bunqasar garin Kaduna, a kullum sai qaruwa take yi. Tana xaya daga cikin manyan birane a wannan qasa. Tsofaffin shugabanni da manyan sojoji da manyan ma'aikata da manyan attajirai na sassan qasar nan a wannan gari suke da zama. Ba domin Kaduna tana tsakiyar Arewa ba kawai, a'a har ma da samun zaman lumana da yanayi kyakkyawa.

Don bunqasar mazauna wannan gari, har ana jita-jitar cewa akwai wata qaqqarfar qungiya mai suna "Kaduna Mafia. " An ce ita ba qungiyar 'yan ta'adda ba ce, a'a qungiya ce ta wasu gaggan mutane waxanda suke kare jarinsu tare da tafi da mulkin qasa. Don haka ne kowane shugaba da ke mulki, dole ne ya saurare

[1] Abdulkarim A.G. MaQarfi, *Sarkin Zazzau: Malam Ja'afaru Xan Isyaku*, shafi na 74

su, ya kuma yi abin da 'yan qungiyar "Kaduna Mafia " suka buqace shi. Saboda suna da qarfin arziqi da siyasa.

An daxe ana wannan jita-jita kan "Kaduna Mafia, " amma har yanzu babu wanda zai ce ga shugaban qungiyar ballantana 'yan qungiyar. Irin wannan bunqasar jama'ar Kaduna da suka yi a Nijeriya, shi ya bai wa Kaduna kwarjini babba. Ko da yake Kaduna ba hedkwatar Nijeriya ba ce, amma qarfin mulkin ta kamar na hedkwatarta yake saboda buwayarta.

Idan aka tare a Abuja, sabuwar hedkwatar Nijeriya, ma'aikatan wannan hedkwata masu yawa daga Kaduna za su riqa zuwa aiki Abuja. Ana jin mai jiwuwa gine-gine da ma'aikatu da kamfanoni, su haxa su cikin 'yan shekaru masu zuwa. To, Allah kaxai Ya san iya bunqasar da Kaduna za ta yi domin ta taso da sa'a da alamar sa'ar a gareta har yanzu!

Kaduna gari ne da komai ya ji. Yana da kamar Kano wajen kasuwanci da Sakkwato wajen sha'anin addinin, Kaduna gari ne mai kama da Enugu da Ibadan wajen wayewa, kuma mai kama da Ikko wajen yawan qabilu sannan kuma ga kama da Abuja wajen da cewar waje ne na masu qarfin iko da nuna qarfin mulkin. Amma bunqasar garin Kaduna sa'a ce ta haxu da dacewa, don haka ya sa jama'a masu qarfi da marasa qarfi suke son zama a cikinsa. Akwai dalilai masu yawa da suka sa yiwuwar haka.

Kaduna gari ne mai kyakkyawan tarihi wanda, Turawa suka kafa, ba tare da an tashi garin wata qabila ba. Saboda yin haka, inji Mista K.J. Bryant zai haddasa gaba da fitinu masu yawa daga baya. Saboda qabilar da aka kora na iya neman tada husuma ta fuskar siyasa, za su ce aba su garinsu ko kuma a biyasu diyya. Garin Kaduna, a bisa tarihi ba shi da wannan illar, saboda haka sai jama'ar su zauna, a matsayin kowa na da 'yancinsa na xan gari matukar yana bin dokar hukuma ba tare da tsangwama ba.

Haka kuma Kaduna gari ne wanda aka kafa a wuri mafi dacewa a Arewacin Nijeriya. Wannan dacewar da Turawan Mulki suka gano, suka kuma yi amfani da ita don su kafa garin da zai zama hedkwatar Nijeriya baki xaya. Kafuwar masana'antu da makarantu sun taimaka sosai wajen qara bunqasar garin saboda an sami qaruwar jama'a wajen hadahadar aiki da kasuwanci.

Matsayin garin a tushen Mulkin Mallaka daga farko da zaman garin farfajiyar Arewa da kuma hedkwatar jiha daga baya sun taimaka wajen kawo jama'a da jawo jama'a zuwa wannan gari. Ko da yake garin Enugu da ke, Gabas da garin Ibadan da ke Yammacin wannan qasa su ne sa'o'in Kaduna, amma ya yi masu zarra sosai, domin kuwa garin ya zama kamar qaramar Nijeriya. Domin garin na xauke da jama'a daga kowace Qaramar Hukuma a Nijeriya. Don haka Kaduna ke ja-in-ja da Ikko tsohuwar hedkwatar Nijeriya ta kowa ce fuska.

A lokacin Mulkin Mallaka, Ikko a matsayinta na hedkwatar Nijeriya, nan ne inda gwamnan Janar yake da zama. Kaduna ma a matsayinta na hedkwatar

Arewacin Nijeriya, a nan ne Gwamna Jihar Arewa ke da zama. Amma Kaduna ba ta da qazanta da cunKwason jama'ar kamar Ikko don haka sai tafi kama da Abuja, wajen tsari mai kyau wadda take a tsakiyar Nijeriya ita kuma kamar Kaduna tana tsakiyar Arewa.

Kaduna za a iya cewa al'umma ce tunbin Giwa domin kuwa ta qunshi al'umomi daban-daban, da qabilu da 'yan qasashe daban-daban. Yawancinsu ma'aikatan gwamnati ne sai dai ma'aikatan masana'antu na qara yawa sannu a hankali – sai manoma xaixaiku.

Kaduna na bunqasa cikin hanzari. A cikin shekarun da suka gabata Kaduna na da yawan mutane xubu arba'in da biyar (45,000) a 1952, amma a shekarar 1967 garin nada mutum dubu xari da arba'in da tara da xari tara da goma (149,910). A shekaru goma da suka wuce, Kakuri 'yar qaramar qanye ce amma a yanzu babban yanki ne na masana'antu. Da yake ana ta ci gaba da kafa masana'antu ana ta raba fulotai. Amma har yau bunqasa Kaduna ke yi babu kama hannu ta kowace fuska.

Cibiyar kasuwanci ta Kaduna sai yaxuwa take yi a babban titin nan na Kaduna zuwa Zariya da aka fi sani da tikin Ahmadu Bello. Yanki ne da ke da gine-gine irin na zamani da suka yi matuqar taimakawa wajen qawata garin. Idan mutum ya taka ta titin Ahmadu Bello ya gangara zuwa ofishin Magajin Gari wato ofishin Kantoma zai yarda cewa Kaduna na ci gaba da bunqasa cikin hanzari. Domin kuwa akan hanyar akwai sabbin gine-gine waxanda yawancinsu benaye (gidan sama) da aka gina su a dama da hagun titin. Ga gine-gine iri-iri na zamani, da kuma na shaguna da kantuna don bunqasar kasuwanci.

Dole ne mutum ya yi hanzarin qarin bayanin cewa gine-gine da Kaduna ke ci gaba da samu ba suna tattare waje guda bane. Sun barbazu ne ta ko'ina. Kaduna na ci gaba da bunqasa ta ko wacce fuska. Misalin wannan shi ne ginin *Lugard Hall* wanda aka gina shi domin tunawa da wannan mashahurin shugaba, wato Lord Lugard. A ginin an yi koyi da tsarin gine-gine irin na Musulmi da ke Arewancin Afirka ta Gabas da Tsakiya. Wannan gini ya qunshi zauren taron Majalisar Dokoki ta yanki kuma yana xaya daga cikin gine-gine da suka fi qayatarwa a Yammacin Afirka, baki xaya a wancan zamani.

Har-ila-yau Allah Ya huwacewa Kaduna arziqin kayayyakin masaqu wacce daga Kano sai ita, wajen muhimmancin masana'antu da cinikayya. Xaya daga cikin irin waxannan masaqu da ke Kaduna ita ce Masaqar KTL (Kaduna Textile Limited). Tana samar da fallen yadi miliyan xari uku da hamsin (350,000,000) a duk shekara, kuma ta xauki 'yan Arewa su fiye da dubu biyu da xari takwas (2,800) inda wasu ke riqe da riqe da manyan muqamai a masaqar. Masaqar Nospin da ke samar da kayan aiki ga masaqanmu na qasa. Bugu da qari, tana samar da kayan haxi na yin "tube " na tayoyin keke da ire-irensu.

Daga *Nospin* sai *Niger Brewery* kamfanin yin kayan sha na kwalba kamar lemun kwalba, da barasa da ke da ma'aikata xari uku (300). Sai kamfanin Qera

Makamai na Tarayya *Defence Industrial Corporation* (DIC) wanda katafariyar ma'aikata cewadda ba kamar ta a wannan kasa, sai Masaqar Arewa (Arewa Textiles), sai kamfanin yin Siminti na Arewacin Nijeriya, sai daffo-daffo na Fetur da ire-iren waxannan ayyuka waxanda aka yisu a yankin Unguwar Masana'antu da ke Kakuri.

Haqiqa ci gaban da aka samu sakamakon bunqasar waxannan masana'antu ba qarama ba ce, domin kuwa tana da yawan gaske, Kaduna ba ta cibiyar kasyuwance babba wille ana iya kwatanta da sauran garuruwa na Arewacin Nijeriya musamman Kano. Ta dai xauki baqi da dama aiki a kamfanoni da masana'antun, daban-daban waxanda suka taimaka wannan gari mai albarka.

Ga xinbin dama ta Inshora a Kaduna. An kafa kamfanoni na Inshora da suka zauna da gindinsu a Kaduna. Wasu daga cikinsu su ne *Royal Exchange* da *New Africa Insurance Co*. da sauransu. Kamfanin Inshora na Kamfanin *Gaskiya Insurance Brokers* – shi ne kamfani na Inshora na farko xan qasa a Arewacin Nijeriya.

Shaqatawa da Watayawa

Wurare da qayayyaki na shaqatawa da watayawa sun qaru matuqa gaya, Otiloli da wuraren shaye-shaye sun qaru. An buxe Otel xin Hamdala a kan kuxi fam miliyan xaya (£1,000,000) da ke da gadaje xari (100) dukkansu da na'urorin sanyaya wuri da xakuna na faranta rai, ga tarho da rediyo, da daqin kallon wasanni na shaqatawa mai kujeru na 'yan kallo guda xari biyu da hamsin (250), da kuma wani vangaren mai xaukar baqi xari biyar (500), da wajen silma da kallon talabijin an ajiye su a kusa da babban xaki. Ko shakka babu Kaduna za ta iya zama tamkar aljannar duniya ga baqo. Sai dai dole in qara da cewa baqin su ne waxanda suka yi imani cewa bambanci na launin fata da harshe a matsayin babban zunubi ne a tsakannin bil'adama.

Har ila yau wata babbar ci gaba ita ce buxe filin wasa na Ahmadu Bello da yaci fam dubu xari takwas (£800,000) wanda wani abin tinqahon ne ga Arewa da a yanzu ya sanya Kaduna ta zama cibiyar harkokin wasa a Arewa. Wannan filin wasa irin na *Olympic* da aka sanyawa sunan Firimiyan Jihar Arewa Ahmadu Bello an buxe shi ne a ranar 2 ga watan Agusta na shekarar 1964. An wadata filin wasan da cikakkun kayayyakin aiki irin matsayin na duniya. Yana xaukar jama'a su dubu talatin (30,000). Ga sabbin kayayyakin wasanni da xakin isar da saqonni ta rediyo da cikakkun kayayyakin aiki da talabijin, da wuraren 'yan jarida, na'urorin xaukar hoto da fitilu na haskaka waje.

Da yake Kaduna na ci gaba da havvaka cunKwason ababen hawa na daga cikin matsalolin da ke ciwa garin tuwo a qwarya, sai dai sannu a hankali ana shawo kan wannan matsala ta hanyar kakkafa fitilu na baiwa ababen hawa hannu a mahaxa ta manyan hanyoyi.

A ci gaba da xaukar matakan sauqaqa cunKwason ababen hawa, an hana masu turin amalanke bin babban titin Ahmadu Bello. Sannan an gama shirin mayar da titin na Ahmadu Bello ya zama tagwayen hanyoyi. Don haka kammala wannan aiki, ko shakka babu Kaduna ta zama xaya daga cikin manyan birane da ke kan gaba a Afirka Kudu da Sahara.

A qarshe, abin da ya yi saura shi ne qarin bayanin cewa bunqasar da Jihar Kaduna keyi babu qaqqautawa na buqatar qwakkwaran tsarin mulki da zai kula tare da raya waxannan vangarori daban-daban. A saboda haka ne haqqin gudanar da harkokin Kaduna a yanzu ya rataya a wuyan sabuwar Ma'aikatar Kula da Al'amura da Harkokin Kaduna.

Garin Kaduna wani tagomashin gari ne, da ya yi zamani mai tsawo, wanda har yanzu ba a samo canjin shi ba. Har yau dai shi ne! Daga hedkwatar Arewa zuwa hedkwatar Jihar Arewa ta tsakiya daga nan sai ya zama hedkwatar Jihar Kaduna da ke haxe da Katsina. A shekarar 1987 da aka qirqiro Jihar Katsina, sai garin ya zama hedkwatar Jihar Kaduna. A duk waxannan lokuta kuwa jama'a sai qara kwararowa suke yi, bunqasar garin kuma na qaruwa. Ko da yake maido da Hedkwatar Nijeriya Abuja na zaizayewa Kaduna bunqasarta a hankali, amma duk da haka wannan gari zai daxe yana jan zarensa.

Gwamna Lugga ne ya kafa garin Kaduna tare da ayarinsa na Turuwan mulki. A dalilin haka ne aka sanya wa wasu layuka da wurare sunan wasu daga cikin waqannan Turawa don tunawa da su.

Mu Tuna da Turawan Mulki

Kaduna cibiyar Mulkin Mallaka ce, tun lokacin da aka kafata a matsayin hedkwatar Arewa. A wannan matsayin ne garin ya zama tushen mulki da Gwamnoni suka zauna wajen tafiyar da mulkin qasar nan. Waxannan shugabanni sun yi amfani da sunayen muqamai iri-iri, kamar yadda tsarin mulkin wancan lokaci ya gabatar, daga wancan lokacin har ya zuwa mulkin kai a shekarar 1959. Daga nan kuma aka samu sauye-sauyen tsarin mulkin qasa, tsakanin mulkin Farar Hula da Mulkin Soja.

A kusan duk waxannan sauye-sauyen mulki, Kaduna ta ci gaba da riqon matsayinta na Kaduna garin Gwamna. Yin taqaitaccen bayani a kan tsarin mulki da sauye-sauyen muqamai, zai taimaka sosai, saboda an qayata sunayen wasu layuka da wurare da sunayen waxannan shugabanni a wancan lokaci. Gwamna Lugga ya riqe matsayin Babban Kwamishina wato *High Commissioner*, a lokacin da ya karvi mulkin Yankin Arewa wato *Northern Protectorate* a farkon shekarar 1900, An yi amfani da wannan muqami daga wannan shekarar zuwa shekarar 1914. Domin tunawa da wannan mashahurin bature, a Kaduna, sai aka sa sunansa a Gidan Shawara wato "*Lugard Hall* " da wani layi a Unguwar Turawa wato "Lugard Avenue. "

Akwai Gwamnoni da aka rubuta sunayensu domin karramawa da kuma tunawa da su, a layuka masu yawa a wannan gari, kamar: Sir Hugh Clifford wanda ya gaji Gwamna Lugga a shekarar 1919 zuwa 1925, da Sir Donald Cameron (1931-1935), da Sir Bernard Bourdillon (1935-1943), dukkansu sun riqe mukamin Gwamna danar a wannan qasa. A wancan zamani kuma masu mulkin lardunan Arewa, ana kiransu da muqamin Leftanan Gwamna ne wato, "Lieutenant Governor. " Waxanda suka riqe wannan muqami sun haxa da C.L Temple daga shekarar 1914 zuwa 1919, da W.F Gowers (1921-1925), da C.W Alexander (1930-1932) da Sir Richmond Palmer. Amma wannan muqamin Laftan Gwamna, an yi amfani da shi ne a Arewa daga shekarar 1914 zuwa 1933. An kuma dawo da amfani da wannan muqami a shekarar 1951. Amma daga watan Oktoba na shekarar 1954 sai Jihan Arewa ta samu mulkin Gwamna na farko.[1]

Nijeriya ta a Kudu, an yi amfani da muqamin Leftanan Gwamna daga shekarar 1914 zuwa 1935; muqamin Cif Kwamishina, *Chief Commissioner* kuma daga shekarar 1914 zuwa 1939. A shekarar 1939 aka raba yankin Kudu zuwa Lardin Gabas da Lardin Yamma, kowane lardi a qarqashin Cif Kwamishina. Amma daga shekarar 1951 wannan muqami ya koma na Leftanan Gwamna, irin na Arewa. An baiwa layuka da damasunayen waxanda suka riqe waxannan muqamai, a garin Kaduna.

Kaduna garin Gwamna Lugga ne, saboda haka ba a bar sunayen jama'arsa da waxanda ya yi zamani da su ba. Kamar Sir William Wallace, wanda ya yi shekaru yana aiki a Kantin Kamfani wato *Royal Niger Company*, ana kuma tunawa da shi har yanzu, musamman a wuraren da ke gavar kogin Binuwai. Haka kuma Sir John Alder Bourdon wanda, yake aikin soja a "Royal Niger Constabulary, " kafin ya shiga aikin gwamnatin mulki a shekarar 1900, ya yi aiki a qasar Sakkwato kafin ya samu qarin girma ya zama gwamnan Ingila a qasar Honduras.

Sir John Eaglesome, wani na hannun daman Gwamna Lugga ne, wanda ya riqe muqamin Daraktan Fidaburdi. Shi ne kuma babban jigon shimfixa hanyar jirgin Baro zuwa Kano, daga shekarar 1907 zuwa 1911. Shi ma an ba wani layi sunansa a Kaduna ta Kudu saboda gudunmawar da ya baiwa Arewa. Akwai layuka da aka baiwa manyan kwamandoji na WAFF, sojojin da Nijeriya ta yi alfahari da su, kamar Kanar James (wanda ya zama Janar kuma Sir daga baya), da Willcocks wanda ya jagorancin, askarawansa da suka yi bajinta a yaqin Ashanti a shekarar 1900. Haka kuma akwai sunan layi, domin tunawa da kanar Morland (ya

[1] *How Roads in Kaduna got their names* by A.K.H Kirk-Greene: Nigerian Citizen, Laraba, April 16, (1958), shafi na 6

zama Janar) wanda shi ne ya jagoranci askarawa da aka tura don su kwantar da tarzoma a lardin Yola a shekarar 1901, da Bauchi da Barno a 1902.[1]

Kanar Strickland shi ma wani gwarzo ne a sojagorancin Arewa a shekarar 1908. Haka kuma Birgediya – Janar Cunliffe wanda ya jagoranci sojojin WAFF a yaqin Kamaru da na *East Africa* daga shekarar 1914 zuwa 1918. Ko da yake an baiwa rundunar WAFF sunan layi a Kaduna, wato "WAFF Road, " amma suna mafi dacewa shi ne RWAFF wato *Royal West African Forntier Force*, saboda qarin "Royal " da rundunar ta samu a shekarar 1928.

A cikin Turawa 'yan Yawo kuwa, Denham ne kawai ya samu suna a cikin layukan Kaduna. Amma sunayen gidan Sarautar Ingila sun sami layuka da yawa kamar: "King George's Way " da layin "Prince Edward " domin tunawa da ziyarar Yarima Edward a shekarar 1925. A shekarar 1956 Sarauniya ta kawo ziyara a wannan qasa, domin haka aka samu "Queen Elizabeth Road " da "Coronation Crescent, " a garin Kaduna. Akwai layuka domin tunawa da 'yan gidan wannan qasaitacciyar masarauta kamar; "Prince Philip road, " da "Edinburgh's road, " da "Magpie road, " wanda sunan jirgin ruwan Duke ne.[2]

Kusan duk an canja sunayen waxannan layuka, daga lokacin mulkin kai zuwa yanzu, *Lugard Hall* yana nan da wannan suna har yanzu. An canja sunan "WAFF Road " zuwa "General Muhammadu Buhari Way," saboda tunawa da gudunmawar da tsohon shugaban qasa, Janar Muhammadu Buhari, GCFR, ya baiwa Nijeriya. Tun daga kafa wannan gari, Kaduna gari ne na Gwamna har yanzu. Haka kuma Kaduna garin Gamji ne.

---

1 *How Roads in Kaduna got their names* by A.K.H Kirk-Greene: Nigerian Citizen, Laraba, April 16, (1958), shafi na 6

2 *Ibid.*

KASHI NA GOMA

A Zamanin Sardauna

Gwamna Lugga shi ne wanda ya kafa garin Kaduna, ya kuma yi masa tsari kyakkyawa da burin ya maida shi hedkwatar Nijeriya baki xaya. gwamnan kam ya cancanci yabo qwarai da gaske, saboda wannan muhimmin abu da ya yi da kuma zaman garin na sai Gwamna ke mulkinsa da kuma qarfin iko na mulki da aka san mazauna garin da shi su suka sa ake yi wa garin kirari da, "Kaduna garin Gwamna. "

Amma babban kuskuren wannan babban Bature, shi ne nuna wariyar launin fata ga mazauna wannan hedkwata. Turawan Ingilishi sun kafa unguwanni biyu domin rarrabe mazauna garin. Unguwar Turawa wato *European Settlement*" da Sabon Garin Doka wato *Native Settlement*.

'Yan Arewa su ne suka kafa Sabon Garin Doka kamar yadda aka ba da labari a baya, don su zauna wurin da ya dace da al'adarsu. Ba a yarje wa kowane xan Arewa ikon zama a unguwar Turawa ba komai iliminsa. A unguwar Turawa inda Turawan mulki ke da muhalli, akwai wuraren wasanni iri-iri na annashuwa. A wannan unguwa ta Turawa ake yin wasannin 'Golf, da Kirket da kuma Polo. Idan ka ga Xan Arewa a wannan unguwa, to, aikin leburanci ya kai shi. Saboda kyawun yanayi, wannan gari sai kullum qaruwa yake yi da baqin Turawa. Idan ka gansu a wannan unguwa ta su, ka cewani vangaren birnin London ne saboda kyakkyawan sakewa da Turawan suka samu. Baqaqen fata masu zurfin Ilimi Nasara ba su samu izinin zama a wannan unguwa ba sai a cikin shekarar 1935.

'Yan Arewa kuwa da suke Sabon Garin Doka, su ne suka zama koma baya, ba a bar su sun sake a unguwarsu ba. Su ne kullum a matse ba su walawa. Jama'a bayin Allah da suka zo daga sassa daban-daban na wannan qasa, an yi masu hani da zama a wannan unguwa. Duk lokacin da suka zo neman fuloti a Sabon Garin Doka sai a ce da su, su tafi can garin Kinkinau su zauna, wai zaman wannan sabon wuri sai wanda aka taso da su daga Dungurun tsohuwar hedkwata. Turawa sun xauki wannan tsattsauran mataki ne don su hana Sabon Gari cika da 'yan Nijeriya.

Tsattsauran matakin da Turawa suka xauka wajen hana Sabon Gari Doka cika da jama'a bai yiwu ba, saboda jama'ar da Turawa suka taso da su daga tsohuwar hedkwata sun yi biris da wannan mummunan mataki don sun ci gaba da bai wa 'yan uwansu da suka zo daga sassa daban-daban na qasar nan masauki. A hankali sai Sabon Garin ya fara cika da jama'a 'yan Arewa.

Bunqasar garin Doka da jama'a ya tayarwa da Turawa rai matuqa saboda dalilai guda biyu. Dalili na farko dai shi ne an tsara Kaduna ne don ta zama

hedkwatar Nijeriya, saboda haka ga hattarar Turawan bai kamata ta cika maqil da jama'ar da xabi'arsu ba ta dace da ta su Turawan ba, kuma idan garin ya cika maqil da jama'a, hayaniyar jama'a, za ta gallabi su Turawan a unguwarsu, sa'an nan tsabtace garin ba zai yi sauqi ba. Saboda waxannan dalilai ne sai Turawan suka xauqi mataki na biyu.

A mataki na biyu da Turawa suka xauka shi ne, kafa sabuwar unguwa domin baqi wato Tudun-Wada a cikin shekarar 1924 kamar yadda aka yi bayani. Yin hakan zai rage jama'a zuwa Sabon-Garin Doka. A taqaice dai Turawa sun dage bisa tabbatar da ganin tsarin nuna wariyar launin fata ya zauna da gindinsa a wannan gari wanda ya taso da farin jini.

Wani abin takaici shi ne, gine-gine don qayatar da garin Kaduna sai suka tsaya cik, ban da tsofaffin gine-ginen da aka yi don tarewa, Turawa ba su yi wa Kaduna wani abin ku zo ku gani wanda zai kawo ci gaban jama'a ba. Abin da suka sa a gaba shi ne kwasar ganimar arziqin qasa da annashuwa kurum. Lallai sun ci sunansu Turawan Mulkin Mallaka! Yan Arewa mazauna cikin garin Kaduna suna cikin mummunan rashin walawa, xaruruwan jama'a da suke son zuwa hedkwatar qasarsu ba su sami dama ba. Ana cikin wannan hali ne Allah Ya azurta Kaduna tare da jama'arta da Firimiya, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardauna Sakkwato wanda ake yi wa laqabi da "Gamji Xan Qwarai. " Da zuwan wannan babban Gwarzo sai ya fahimci abubuwan da suke gallabar garin da mutanen cikinta, saboda haka sai ya yi namijin qoqari wajen kawar masu da su. Ga abin da Gamji ya ce game da Kaduna da jama'arta:

> *Na tabbata cewa Kaduna ita ce farfajiyar wurin ciniki a duk Nijeriya ta Arewa A nan ne ma wani lokaci wakilan jama'a su kan zo don su yi shawara a majalisa. A nan ne kuma Sarakuna waxanda ake yi wa Majalisunsu na En'e jagora, su kan kuma zo su yi shawarwari a tasu Majalisar da sauran taro iri-iri. A nan ne kuma shugabannin ma'aikatun gwamnati ke dai-daita shawarwariin irin kayan aikin da za ta saya don kyautata ci gaban Jihar nan.*
>
> *Mu, gwamnatin da ke zaman Kanta, mun qawata garin da kyawawan gine-gine muna kuma sa rai mu ga manyan kamfanonin ciniki su masun yi haka nan. Amma don gine-gine su kaxai ai ba su isa ba. Wajibi ne a tafiyar da al'amuran hedkwatar nan yadda ya kamata, jama'ar da ke cikinta su kasance suna masu farin ciki da wadatar zuci.*[1]

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 213

Idan mutum ya dubi ayyukan da Gamji ya yi wa Kaduna ta fuskar qayatarwa a cikin shekaru qasa da goma, da kuma matakan da ya xauka na tabbatar da cewa mazauna garin suna masu farin ciki da wadatar zuci, lallai ne a yabawa wannan babban gwarzo. Sardauna ya rusa tsarin Mulkin Mallaka ya maida garin Kaduna Farfajiyar Arewa, wadda kowane xan Arewa zai yi alfahari. Don haka a ke wa garin laqabi da Kaduna garin Gamji. Sardauna ya yi abubuwa masu yawa da suka bunqasa garin, suka kuma kawo wa jama'ar garin ci gaba ta fannin ilimi da kasuwanci da ayyukan gona sana'a da siyasa. Wannan littafi ba zai xauke duk abubuwan ba, amma ga kaxan daga cikin waxannan abubuwa. A nan ne ya kamata mu ba da takaitaccen wannan shahidin.

Sir Ahmadu Bello

Alhaji Sir Ahmadu Bello, GCON, KBE, M.H.A, GCFR, Firimiyan Jihar Arewa an haifeshi ne a garin Ravah kusa da Sakkwato a ranar 12 ga watan Yunin 1910. Kuma mahaifinsa Malam Ibrahim Hakimin Ravah jikan Muhammadu Bello xan Shehu Mujaddadi Usmanu ne. Ya fara makarantarsa ta Elementary a Makarantar Lardin Sakkwato a zamanin mulkin Mai-Turare.

Abinka da mai maxaukakkiyar daraja sai nan da nan Ahmadu Bello ya kammala karatunsa na ilimin Addinin musulunci ya kuma tafi qaro ilimi a Kwalejin Katsina a shekarar 1922. To, a cikin shekarar 1930 ya kammala karatunsa sai Hassan xan Mu'azu ya naxa shi Sarkin Ravah inda ya gaji mahaifinsa ya zama Hakimin Ravah. An naxa shi sarautar Sardaunan Sakkwato a shekarar 1938 bayan rasuwar Hassan. A kuma wannan lokaci ne Sir Abubakar na III ya gaji sarauta.

Bisa al'ada dai mai muqamin Sardauna shi ne kan gaba a fagen yaqi shi kuma shi ne ke buxe wa Sarki hanya ya kuma yi wa ya'yan Sarki jagora. A fagen fama kuma idan yaqi ya yi muni shi ke kare Sarki. Don haka ake yi masa kirari da cewa "Jarumi Mai Takobi " ko kuma a ce da shi "Jarumi mai buxe Kofa. " Ka ga ke nan wannan Sarauta ta "Sardauna" ba a baiwa kowa sai jarumi amintacce mai gaskiya da riqon amana. A duk waxannan halaye Ahmadu Bello ya yi fice.

Hasali ma dai wannan sarauta ta Sardauna sai ta qara masa qaimi wajen nuna jurewa da wahalhalun jama'a da kuma riqe su bisa gaskiya da adalci. Amma a baxini kuwa wannan muqami ya yi masa kyakkyawan shiri don ya xauki Arewa baki xayanta a matsayin "Sarki " da zai kare Arewa da qarfinsa da kuma jininsa. 'Yan Arewa kuma sai suka zaman "Ya'yan Sarki" da Sardauna zai wa jagora bisa so da qauna da adalci. Saboda haka ne muqamin "Sardauna" sai ya sauya launin kamar hawainiya ya koma muqamin"Firimiya." Allahu Akbar! Allah Mai Iko Buwayi gagara misali. Wannan 'jarumi mai buxe kofa' sai ya buxewa Arewa kofofin ci gaba.

A shekarar 1948 aka zavi Ahmadu Bello ya zama Wakilin Sakkwato a Majalisa ta Kaduna. A wannan shekara ce ya tafi Ingila a qarqashin wani shiri na 'British Council'. Ya isa Ingila ran 10 ga watan Janairun 1948. Tafiya mabuxin. Cikin Ikon Allah sai ga Sardauna a Ikko a shekarar 1949.

Waxannan tafiye-tafiyen sun yi tasiri sosai a rayuwar wannan Gwarzo. A zuwansa Ingila ya qaro ilimi, ya kuma qara wasa qwaqwalwarsa da kaifin basirarsa a wajen mulki da tafi yar da harkar jama'a. Tafiyarsa Ikko ma na da muhimmanci sosai. A wannan hedkwatar Nijeriya ya sadu da manyan 'yan siyasa da 'yan gwagwarmayar neman 'yanci. Amma zuwansa Ikko ya qara nuna masa matsayin siyasa a Nijeriya, ya kuma hangi tasirinta a Arewa. Har ila yau, ya hango da idon basira cewa, Arewa za ta faxa wani mummunan matsayi, idan ba a a fargar da jama'arta cikin hanzari ba. Saboda Arewa a wancan lokaci ita ce koma bayan sauran jihohi.

Hasali ma dai, idan Wakilan Arewa suka tafi taro a Ikko, a kan yi masu ihu wani lokaci ma har jifansu ake yi don a nuna masu cewa ba su isa ba. Ana son a hassalasu, a rikirkita masu shirin da suka shigo da shi Ikko. Amma ko kaxan wannan hali bai sa su Sardauna sun fusata ba, a maimakon haka sai suka qara masu qaimi don su himmatu wajen haxa qarfi da karfe, don a qwato Arewa daga kwazazzabon duhun kai da take ciki, waxanda **CI UKU**, wato Zalunci da Lalaci da Jahilci suka jefa ta. Wannan mummunan matsayi kuma zai jefa jama'arta cikin bauta a Tarayyar Nijeriya, za a kuma mai da su qyale-qyalen huhun-ma'ahu.

A cikin shekarar 1951, Sardauna ya zama Ministan Ayyuka a cikin gwamnatin Jihar Arewa. Ya kuma zama Ministan Qaramar Hukuma da ci gaban jama'a a shekarar 1953. Duk waxannan muqamai da ya riqe sun taimaka masa wajen gogewa a kan sha'anin mulki da jurewa wajen xaukar nauyin wahalhalun jama'a tare da wayewa sosai a siyasar Nijeriya.

Saboda gogewarsa sai yafi kowa dacewa da shugabancin Wakilan Arewa a Taron Shawara a London wato *Constitutional Conference in London* a shekarar 1953. A kuma shekarar 1954, a taron Jam'iyyarsa ta Qungiyar Mutanen Arewa wato *Northern People's Congress* (NPC) aka zave shi Shugaban Jam'iyya.

Sardauna Ya Zama Firimiyan Farko

Jumma'a, 1 ga Oktoba, a xakin Majalisar Ministocin Jihar Arewa, aka rantsar da Mai girma Mr. H.R.E. Browne, aka naxa shi Muqaddashin gwamnan Jihar Arewa, da qarfe takwas na safe. A wurin, akwai Ministocin jiha da sauran gaggan gwamnati. Daga qarfe 8.45 zuwa 9.15, Muqaddashin Gwamna, Ministocin jiha, Sarkin Kano, Sarkin Abuja, wakilan Majalisar Wakilai, jama'a dubbai, Turawa da Baqar Fata, Larabawa da Qwara, suna Barikin Mogadishu, inda soja suka yi rawa, don wannan rana. Muqaddashin Gwamna, yana tsaye a dakali, tare da Birigediya Hill, babban kwamandan sojojin Arewa, ya karvi gaisuwarsu. Da qarfe 11,

Muqaddashin Gwamna ya isa bakin qofar *Lugard Hall*, a kan bene na qofa, a gaban 'yan Majalisar Ministoci da dubban mutane, maza da mata, yara da manya, Turawa da Baqar Fata, Larabawa da Qwara, ya naxa Sardauna Ahmadu, Firimiyana farko, a Jihar Arewa. Dubban jama'a, waxansu a motoci, waxansu a qasa, aka raka Firimiya gida.

Da qarfe 3.15 na Yamma Muqaddashin Gwamna ya yi wa jama'ar Arewa jawabi a rediyo Da qarfe 7.15 aka sake babban taro a *Lugard Hall*, aka yi dinar Firimiya Qarfe 9 Firimiya ya je gidan rediyo, ya yi jawabi zuwa ga mutanen Arewa. Kashegari, a xakin Majalisar Ministoci, aka rantsar da Ministoci, aka naxa su, domin da can sun yi 'yan waxansu mintoci, rawunansu na warware tukuna, sai da aka naxa Firimiya, sa'an nan ya sake naxa su. A ran nan ne kuma aka naxa M. Muhammadu Inuwa Wada Kano, ya zama Sakataren Majalisa na Firimiya, wato *Parliamentary Secretary*.

Tun ran Alhamis ake ta sha'anin bukukuwa iri-iri, Jama'a da yawa sun taru a gidan Sardauna suna taya shi murnar farin ciki da zuwan wannan rana. Daga nan sai jama'a suka runtuma zuwa gidan Malam Ibrahim Dasuqi, sakatarensa. M. Ibrahim ya ce, da wani xan jarida 'Madalla, na sami abokin zuwa kallon wata rawa, wai ita *Constitution Dance*, wadda *Kaduna Ladies Social Club* za su yi, don murnar samun Sabon Tsarin Mulki. Sardauna, Alhaji Isa Kaita, M. Nagwamatse da sauran manya, can suka same mu. Badujala da begiloli suka fara motsi, maza da mata suka dadumi juna, suna kewayawa. Amma sai bayan tafiyar Sardauna rawar ta ruguntsume sosai. An kwana ana rawa.

Tun wajen qarfe takwas na safe dubban mutane suka kewaye filin fareti na Barikin Mogadishu, waxansu a zaune a kujeri, waxansu a tsaitasaye, waxansu kan bishiyoyi, soja jingim sun jeru, ga 'yam badujala a bayansu, ga bataliyar sojan igwa da motoci suna xauke da igogi, duk Muqaddashin Gwamna a ke jira, Mai girma Mr. H.R.E. Browne. Qarfe takwas dai-dai aka naxa shi wannan matsayi a xakin Majalisar Ministocin Jihar Arewa, a gaban Ministoci da sauran manyan da suka cancanta su je can.

Muqaddashin Gwamna ya iso a motarsa, da qarfe 8.45, tare da Sakatarensa, soja 'yam babur sun yi masa banga-banga. Ya tsaya bakin dakalin da Birigediya Hill da ajitan nasa su ke jiransa. Suka jeru a dakali, soja suka yi taken Sarauniyar Ingila, sa'an nan Muqaddashin Gwamna da Birigediya Hill suka hau wata mota jeep. Birigediya yana tare da direba Bature, shi kuwa yana bayan mota a tsaye. Haka suka kewaya soja, kowa na kallonsa.

Da suka komo, suka hau dakali, Muqaddashin Gwamna ya raba wa sojoji Turawa da Baqar Fata, lambobin da suka samu na daxewa a soja suna kyakkyawan aiki. Baqar Fata dai, su ne Samanja Long, Rajimanti Umaru Numan, Saje Dogon Yaro Filinge, Kofur Usman Gwambe, Kofur Hassan Yerwa, Laskofur Hassan Katsina-Ala da Tom Dikwa.

Yana rabon lambobin, mutane suna ta tafi, har ya gama. Daga nan, rundunar motoci na gaba, janye da igogi, soja na biye a baya, suka wuce kusa da dakali, suka gai da Muqaddashin Gwamna. Suka kewaya wurin tsayawarsu, sa'an nan suka sake yin maci, sun yi banga-banga, suka yi gaisuwa, ya karva. Sai aka yi taken Sarauniya, Muqaddashin Gwamna ya shiga motarsa, ya koma gida. Amma jama'a ba su bar wannan waje ba sai da soja suka yi maci zuwa barikinsu, sa'an nan suka bar filin. Mutanen da suka je kallon faretin nan, sun kai dubu ashirin (20,000)!"

Mutane da yawa, ko da yake ba za a fara komai ba sai qarfe goma sha-xayana safe, daga wurin fareti, sai suka wuce kai tsaye zuwa filin qofar *Lugard Hall*, inda za a yi bikin naxa Mai girma Sardauna, Firimiyana Jihar Arewa. A wannan waje kuwa, mazaunin manyan baqi yana Yamma cikin filin. Jerin kujeri na Gabas kuwa, yawanci 'yan Majalisar Wakilai ne. A Gabas da kujerin Wakilai, a qetaren titi, akwai 'yan NPC Mata, da Samarin NPC da sauran mambobi da suka zo daga Zariya da sauran wurare, domin idonsu ya gane musu an naxa babban shugabansu, Firimiyan farko na Jihar nan.

Da qarfe 10.38 na safe Mai girma Sardauna ya iso, tare da sauran Ministocin jiha. Sardauna yana sanye da wandon kamun qafa, fari tafkeke, ya sa riga ta farin alharini, da alkyabba ja, mai aikin dusar zinariya fara, ya cika alkyabbar taf. Ya naxa shuxin rawani, mai aikin farar dusar zinariya. Minista Alhaji Yahaya Madawakin Ilori, da Alhaji Aliyu Makaman Bida duk sun yafa alkyabbu. Nan suka tsaya a qofar *Lugard Hall* suna jiran zuwan Muqaddashin Gwamna. Sarkin Kano Alhaji Muhammadu Sunusi da Sarkin Abuja Alhaji Umar Sulaiman suna saman benen qofa, inda za a yi sarautar.

M. Umaru Gwandu, akawun Majalisar Wakilai da M. Muhammadu Tukur Yawuri, akawun Majalisar Sarakuna, su ne da aikin shirin fili. Sai kaiwa su ke suna komowa. A lokacin, lallai mutanen da ke wurin sun doshi dubu goma (10,000) soja sun shigo filin, tare da makaxansu, sun qame suna jira. Ma'aikatan rediyo, su Darakta Mr. Wilkinson da M. Ladan suna bene, sun shirya wayoyi, yadda kowa zai ji abubuwan da za a faxa. Baturen ofishin ba da labari, babbansu, Mr. Hindle, ya haye kan rumfar mota, yana xaukar sinima ta wurin da masu zuwa.

Muqaddashin Gwamna na isowa, Sai M. Umaru Gwandu ya zabura ya buxe masa mota, ya fito suka gaisa da Birigediya Hill, sa'an nan soja suka yi taken Sarauniya, kowa yana tsaye, Muqaddashin Gwamna da dukan Turawan da ke cikin kayan Sarki suka sara. Daga nan yakewaya soja, ya dawo ya tsaya aka sake kaxa take, sai kowa ya miqe ya qame.

Daga nan sai Mr. Browne ya shiga *Lugard Hall*, ya hau benen qofa, kowa na ganinsa. Ga abin rediyo mai qara girman murya, ya fara jawabi Sardauna na zaune daura da shi a tebur. Sa'an nan Sardauna ya miqe, Muqaddashin Gwamna ya miqa masa takardar iznin naxa shi Firimiya, jama'a suka yi tafi, suna murna.

M. Isa Wali ya karanta fassarar jawabin nan da Hausa, sa'an nan Sardauna ya miqe, jama'a suka qara varkewa da tafi, ya amsa. Ya fara da Hausa, yana qarewa, ya yi savi zarce da Turanci.

A bisa yadda shirin yake, Sardauna ne zai zavi waxanda za su zama Ministocinsa na jiha, tare da yardar Gwamna. Cikin jawabin Sardauna, ya ce,"Mai girma, ka yardam min, mataimakan nan namu, Ministoci, su ci gaba, har ma ka qara mana da xan Karimin Sarkin nan da ya rasu, ya zama minista mai ba da shawara. Shi ne Sarkin Kano, Alhaji Muhammadu Sunusi wanda bana ne ya gaji tsohonsa, ya zama Sarkin Kano. Sardauna ya zana sunayen Ministocin jiha guda tara, wato saura guda uku ke nan da za a naxa nan gaba. Cikinsu biyu masu riqe da ayyuka, guda mai ba da shawara. Mun ji qyas, su waxannan sai bayan an qare zaven zuwa Majalisar Nijeriya, sa'an nan za a naxa su.

Sa'ad da Muqaddashin Gwamna ya sauko za shi gida, lallai jama'ar da ke wurin nan sun kai dubu goma sha-biyu (12,000). Soja suka kaxa taken Sarauniya, ya karvi gaisuwa, ya shiga mota ya koma. Can Sardauna ya bunqaso, dubban mutane, waxansu a motoci, waxansu a qasa, waxansu a kekuna da su babur, har sun gama da gidansa, kafin ma shi ya shiga motarsa a *Lugard Hall*. Kaxe-kaxe da bushe-bushe, waxannan babu mai jin na wani. Jerin gwanon jama'a kuwa ai sai wanda ya gani.

Daga *Lugard Hall* zuwa gidan Sardauna, lallai bai yi mil guda ba, amma sai da aka yi minti arba'in a mota kafin a isa. Jama'a har sun yi dafifi a gidan Sardauna, duk wanda ya isa zai tarar an cika, an cika. Mutane kamar tururuwa, danqam, suna shiga suna fita, suna yi wa Mai girma Allah Ya riqa. Duk wanda ya zo, Sardauna yana hannu da shi. A wannan lokaci mutum idan ya dubi ximbin mutanen da su ke son masafaha da shi, sai ya zaci kafin ya qare, hannunsa zai xaxe. Haqiqa jama'a sun yi murna da farin ciki da wannan muqamin da Sardauna ya samu.

A cikin wannan haline sai jama'a suna ta kuwa,"muna son ganin Sardauna!" Sai ya hau kan fafarandar benensa, ya tsaya. Nan 'yan NPC maza da mata suka yi ta karanta masa waqoqin da suka yi masa. Daga nan sakataren reshen Zariya ya karanta saqon murna da suka yi masa. Ciki ya ce,"Qasar nan da ma hannun Shehu Usumanu ta sami qasaitarta."To," in ji sakatare,"ga Shehu Usumanu ya dawo!"

Dafaxin, wannan kalami ya jawo tafi! Cikin amsawar da Sardauna ya yi, ya ce,"Su Shehu Usumanu da sauran mazajen farko, babban abin da suka sa a gaba, wanda ya zaunad da su cikin matsayinsa, shi ne gaskiya. Mun yi niyya, ku kuma jama'armu duka ku yi niyya, komai za ku yi, ku yi gaskiya." Sardauna ya ce aikin da za su yi, shi ne su ga Arewa da mutanenta sun koma kan matsayin nan nasu na girma da mutunci."Amma," in ji Sardauna,"babu abin da mu za mu iya yi, sai da goyon baya daga gare ku, jama'a." Yana qarewa, wurin ya ruxe da kiran"salama, salama, salama!" Sardauna ya ce,"Allah Ya ba mu salama." Amin.

Da almurun fari sai xaruruwan jama'a suka tasam ma *Lugard Hall*. Don su halarci walimar da Sardauna ya shirya ta musamman. An yi ruwa, don haka dinar da za a yi, tilas sai a xaki aka yi shagalin wannan walima. A bakin qofar xakin Majalisar Wakilai, 'yam badujalar soja, sun ci ado, ga wani bimasta yana ba su aiki, sun ruguntsume da kaxe-kaxe. Ga Turawa, ga Baqin Mutum, manyan Arewa, ga Larabawa ga Qwara, sun cika. Kowa yana riqe da kwaf, ko sigari, ko kuwa bakinsa na motsi, ya cika shi da wani abu mai daxi.

A wannan lokaci sai ka ga kowa na kewayanan, yakewaya can, yana taxi da mutane. Kowa yana harka da raha. Masu xaukar hotuna, sai walqiya ka ke gani. Falauu, Faal, hoto na xauka. Qarfe 8.30 na dare aka ce za a tashi. Laifin daxi qarewa, jama'a kam sun ga saurin cikar lokacin nan. Waxanda suka shantake can bene wajen shagali suka sarqe da taxi, sai suka ji gon, gon, gon, ana buga gwarje, wai su tashi lokaci ya yi. An ci, an sha, am busa hayaqi, an ko yi taxe-taxe. Abin ya yi kyau ainun. Kwalliya ta biya kuxin sabulu.

Sardauna mutum ne mai barkwanci da son raha sosai. Ranar da ya haxu da wakilin jaridar Gaskiya Ta fi Kwabo da zuwansa, sai Sardauna ya ce,"Da na gan ka har gabana ya faxi." Sai wakilin jaridar ya ce,"Sabo da me, yallavai?" Ya ce,"Tsegumi gare ka. Wada Allah Ya yi duk abin da mukai kwashewa shi kai shi barbaxa wa duniya." Xan jarida ya ce,"Ai ko sai dai a yi ba mu gani ba, ko a faxa ba mu ji ba. Amma im mun ji mun gani, duniya ta ji. Balle fa in abin alheri ne irin wannan da ya sami Arewa da jama'arta."

Ran Asabar, Wakilin jaridar ya sami Sardauna a gida. Firimiya ya ce,"Me ya kawo ka da wuri Haka nan?" Wakilin Gaskiya ya ce,"Na zo neman labari." Sardauna ya ce,"Na me?" Ya ce,"Na abin da ya faru da safen nan." Sardauna ya ce,"Taho. Dubi wanga agogo, abokan aikina, manya da yara suka saya, suka aza mini shi bisa tebur, da sunayensu. Wanga yan nuna sun yi farin cikin aiki da niya. Agogon yana da kyau. Yana iya zama a tebur, qarami ne fa. Yana iya zama agogon aljihu. Ana iya riqe shi a hannu. Yana da wuta, yana da qararrawa.

Jumma'a 1 ga Oktoba 1954 nada muhimmacin gaske a tarihin Jihar Arewa. A ran nan ne aka rantsar da Ministoci, ko wanne aka naxa masa rawaninsa. M. Muhammadu Inuwa Wada kuwa aka tabbatam masa shi ne Sakataren Majalisa, *Parliamentary Secretary*, na Sardauna. Wato ma'anar wannan, shi ne in Sardauna ba yanan, maganar aikinsa majalisa za ta neme ta a hannun M. Wada ne. Kai, Allah Ya riqam musu su duka.

Ran Jumma'a 1 ga Oktoba, da qarfe tara na dare, Firimiyan Jihar Arewa, Mai girma Sardaunan Sakkwato Ahmadu, ya yi wa jama'ar Arewa jawabi a cikin rediyon Jihar Arewa. Ga jawabin:

Godiyarmu ta tabbata zuwa ga Ubangijinmu, yabo ga AnnabinSa mai tsira da amincin Allah da ya kawo mu ga wannan muhimmiyar

rana a cikin tarihinmu. Na ce muhimmiyar rana saboda yau xin nan Arewa ta komo ga matsayinta na 1907 – 1914, wato ta sami gwamnan kanta. Qari da daxawa ta sami Firimiyana farko da da ba ta tava samu ba. Sabo da wannan fa da sauran baiwa, wadda Allah Ya yi mana, ko ina a Jihar nan a ke ta shagulgula. Wannan ita ce alamar shigowar Sabon Mulki. Muna ko roqon Allah shi bishe mu hanyar salama, kamar yadda ya biyo da mu nan baya. Godiyarmu ta tabbata zuwa gare shi.

Na tabbata dukkan masu saurare na za su yarda da ni, cewa a qalla zuwan Turawa nan qasar ya kawo mana zaman lafiya, ya kuma zafafa mana shari'a ta adalci. Kuma ba ni zaton akwai mai musun cewa, cikin shekarun nan 50, zaman jama'armu bai kyautatu fiye da na iyayemmu ba. Amma fa duniya cewadda ke tafe a gurguje, dole mu kuma mu sheqa tare da ita.

Abin ban takaici shi ne duk daxewan nan, Arewa ba ta sami shiga cikin zancen siyasar qasar nan ba, sai cikin shekara bakwai kawai da suka wuce, kun ko san wannan xan taqaitaccen lokaci ne. Amma duk da haka mai hankalin da ke biye da yadda al'amuran Nijeriya ke tafiya, ya san Arewa ta yi abin yabo a cikin xan guntun lokacin nan.

Gurbin da ke akwai mun rufe shi, ga kuma Sabon Shirin Mulkimmu, wanda ya ba mu dama mu 'yan Arewa mu tafiyar da al'amurammu da kammu. An fa ba mu dama, damar ko lallai za mu yi amfani da ita. Yanzu za mu matsa zancen ilimi ko ta wace hanya, har mu ga babu sauran kafar da za a bi a ce mana muna baya. Haka kuma lallai za mu tsaya mu ga 'yan Arewa su ke riqe da ragamar Arewa.

Amma fa duk irin ci gaban da za mu yi, za mu yi qoqarin riqe kyawawan al'adunmu, yadda ba za mu vata tarihinmu ba.

Yanzu zan koma ga wata babbar magana, wadda ke qunar zukatan mutane, ita ce maganar mulkin kai. Ni dai ban tava sanin wani xan Arewa da ba shi son mulkin kai ba. Ni, sai in ce duk qasar nan babu wanda ya fi mu son mulkin kai, don ko da Turawa suka zo qasar nan, an same mu muna mulkin kammu.

Abin tambaya guda ne cikin wannan magana "wane irin mulkin kai mu ke so?" Ganina mulkin kan da mu ke so, shi ne mulkin kan da im mun amshe shi, ba za mu yi da na sani ba. Wannan ko ba shi samuwa, sai mun janye damtsenmu. Tilas mu sake hali, mu xauki halin bauta don qasarmu, kuma game da shi wannan halin, mu qara da ba waxansu abubuwa baya.

Yanzu ita wannan gwamnati tamu, ta sa gabanta kan qara wa jama'a ilimi, qarin asibitoci, qarin samun abinci ga jama'a da kayan

gona na samun kuxi, qara samun sakewa game da gatance-gatancen siyasa da kyautata zaman jama'a duka gaba xaya ba sai Wane da Wane ba.

Cin nasararmu game da wannan nufa tamu ya danganta ga gudunmawarku ta sa himma ga ranku, da kuma hana ranku waxansu abubuwa da ku ke so, kamar yadda ita ma gwamnatin ke hana kanta. Da haka kawai za mu tafi tare, muna bauta wa qasar nan, ba wai don mu al'umma ta yanzu ba, a'a, har da ta bayanmu.

Zan jirkita ga wani xan gargaxi da ni ke son yi ga abokaina 'yan siyasa cikin ko wace jam'iyya ko su ke. Akwai babban haxari ga qasa, wadda ke sabuwar shiga cikin siyasar zamani kamar tamu 'yan siyasa su xauki suka mai rushe qasa, ta fi mai gyara amfani.

Da yawa waxansu xanyun 'yan siyasa na qasar nan ba su sa komai gaba ba, sai haddasa qiyayya da karya doka ga 'yan waxanda suka samu suka yarda da su. Ba su da wata katamammiyar hanya da jama'a za su saurara wa, don haka wa'azinsu sai ya zama gamin qiyayya, xan'uwa ya qi xan'uwansa wai saboda siyasa kawai. Irin wannan abu babu inda zai kai mu sai ga hargitsi da rashin shugabanci, har fa in qabilu sun rarraba. Wannan ko, shi zai naqasa tarihinmu, da al'adunmu da ma addininmu.

Don Allah kada mu mai da wannan tabi'armu, mu kula fa da masu wa'azin da ba su aikata wa'azinsu. Ina roqon kowane xan Arewa mai sonta tsakani da Allah, ya yi qoqarin haxa kan 'ya'yanta da qulla zumunta tsakaninsu. Ya yi iyakar zarafinsa ga kyautata sunanmu da darajammu da aka sani ta tsare oda da rashin son tashin hankali. Ta haka kawai za mu sami kyakkyawar daraja daga sauran qabilu da kuma girmamawa cikin al'umma da ke qarqashin tutar mulkin Ingila.

To, jama'a, tun da Allah Ya kawa mu wannan matsayi na Arewa na yau, ya kamata mu bayyanar da godiyarmu ga waxanda suka yi renonmu har muka sami kawowa gare shi. Ban da su, waxanda suka aza mana harsashin gininmu wajibi ne mu gode ma mashawartanmu da sun halarci taron Shirin Mulkin da aka yi a London da Ikko, suka samo mana wannan nasara.

Godiyata kuma kullum ba za ta qare ba zuwa ga 'yan Majalisar Zartaswa ta Arewa da Ministocimmu 'yan Arewa na Ikko, don dukansu sun yi aiki ba tsaitsayawa, kuma suna kan yi, don dai su ga mun kai ga manufan nan tamu ta qarshe, wato mulkin kai kyakkyawa.

Haka kuma ba za mu manta da Sarakuna da majalisun su ba, ga ba da godiyarmu saboda qoqarinsu da himmarsu kan tafiya tare da

lokaci. Godiyata ta qarshe zuwa ga dukkan jama'ar Arewa, waxanda da ba da xa'arsu ba, dukkan waxannan abubuwa da ba za su yiwu ba.

Maganan nan da ni ke yi ita ce ta farko ga sabon matsayina na Firimiya, ina ko yinta ne zuwa ga dukkan jama'ar Arewa, don yau ina jin Allah Ya maishe ni makiyayinku hadiminku. Haqqin jama'an nan ya xoru kaina, zan ko yi iyakar zarafina da yardar Allah in ga buqatocinku sun biya.

Ina roqon Allah Maxaukakin Sarki Ya ba ni iko da qarfin xaukar wannan babban alhakki, yadda Arewa za ta zauna lafiya ta kuma sami wadata, jama'a su zauna babu wata qiyayya tsakaninsu, ko don bambancin girma, addini, launi ko qabila.

Allah Ya yi maku albarka, ya sa kuma mu gama lafiya, amin.[1]

Haqiqa mu duka sai mu ce amin! Sardauna ya xauki amana mai nauyin gaske, wadda rabon da a sami wani xan Arewa guda xaya tak da ya xauke ta a kafaxunsa shi kaxai, yau wajen shekara hamsin ke nan. A zamanin da, duniyar ba irin ta yanzu ce ba. Idan da za a fito da wani mutumin da ne, a saukar da shi cikin tsakar gidansa, wataqila da kyar zai iya shaida gidan, balle unguwarsu, balle garinsu, balle fa waxansu qasashe da ya sani cikin halin rayuwarsa.

Komai da komai ya juya. Zamani ya juya, mutanen cikinsa ma sun juya. Ko a zamanin da, lokacin da abubuwa iri-iri su ke zaune lafiya, lokacin da jama'a su ke ta biyayya ga na gaba, babu wata tambayar dalilin yin abu kaza, ko dalilin rashin yinsa, babu abin da ya fi riqon jama'a wuya. Balle yanzu.

Yanzu zamani ya kai inda ya kai. Arewa ta juya, juyi mai saurin gaske cikin 'yan shekaru kaxan. Kawunan mutane sun waye fiye da yadda kowa yake tsammani. Komai mutum ya yi, akwai waxanda za su iya tambayarsa dalili. Duk abin da bai yi ba, akwai masu iya tambayarsa dalili.

Irin Arewar da take hannun Sardauna ke nan yau. Ta bambanta da irin wadda shugabanimmu, kakanninsa, suka riqe. Amma, kamar yadda Mai girma Mr. Browne ya ce ne, mun sani Sardauna zai yi matuqar qoqari ya tafiyar da komai ga matuqar amfanin Jihar nan da mutanenta. Mu ma muna fata zamaninsa ya zama na farin ciki ne, da wadata. Amin.

Jawabin Muqaddashin Gwamna

Jumma'a, 1 ga Oktoba, ranar da aka soma aiki da Gyararren Tsarin Mulkin Nijeriya, kamar yadda kowa ya sani ne, rana cewadda aka yi shagulgula da yawa a cikin Jihar Arewa. A wannan ranar ce Jihar Arewa ta sami abin da rabonta da

[1] GTK 6/10/1954, shafi na 6.

shi, yau kamar shekara arba'in wato Gwamna. Har ila yau, a ran nan ne Arewa ta sami abin da ba ta tava samu ba – shi ne Firimiya.

Xanta na cikinta, halak malak, Sardaunan Sakkwato Ahmadu, shi aka naxa. Ran nan da Yamma, Muqaddashin gwamnan Jihar Arewa, Mai girma Mr. H.R.E. Browne, ya je babban gidan rediyon jiha a Kaduna, ya cewa Arewa:

Yau, rana ce abar tunawa a cikin tarihin Jihar Arewa. Sabili da shigowar Gyararren Tsarin Mulki, da naxawar Firimiya, an sake kaiwa wani matakin ci gaba, a game da sha'anin tsarin mulki a Jihar nan, alhali kuwa mutanen Jihar suna da hali mafi yawa, wajen tafiyar da sha'anin Jihar. Amma fa a gane, kyakkyawar gwamnati, ba tana vuvvugowa ne ba kawai daga cikin sabon Shirin Mulkin, wanda ya dai-daita da zamani. Ko mun sami kyakkyawar gwamnati, ko ba mu samu ba, wannan zai danganta ne ga ko wannemmu.

Misali, zai danganta ga mai zave, lokacin da ya yi quri'arsa, zai danganta ga majalisar mulki, lokacin da ta yi dokokinta, sa'an nan zai dangarta ga gwamnati, lokacin da suka gudanar da irin abubuwan da aka shirya a yi.

Lelle ne a manta da bambancin qabila, domin samun zama lafiya da arziqi na jiha. Lallai ne a haqurcewa juna, a game da sha'anin addini. A guji yawan ta da hargitsi ko waxanne iri. Babu abin da za a samu da hargitsi, iyakar abin da zai faifar, shi ne qiyayya da vacin zuciya. In kana buqatar faxar ra'ayinka, ba lallai ne sai ka ruxe ba, haba, kana iya aikawa da ra'ayinka ga majalisunku da majalisun wakilanku. Ko a da can an sha cewa Qasa fa ta kan sami kyakkyawan gwamnati irin wanda ta cancanta ne kaxai. Wannan magana ko sau nawa aka ma'maita ta, dai-dai ne.

Shi kansa gyararren Tsarin Mulkin nan ya tabbatar cewa mutane da irin buqatunsu a cikin jihohin nan uku, ba duk xaya su ke ba. Don haka an kwaso ayyuka jingim daga hannun gwamnatin Nijeriya, am miqa wa gwamnatin jihohi. Wannan zai bai wa ko wace jiha sukunin faxa sha'aninta ta hanyar da ta dace da ita, amma duk da haka, in an ce za a yi ta kambama irin bambancin da ke tsakanin jihohin, zai zama kuskure babba. Don kuwa, bai kamata mu manta ba ko qanqane, cewa ko wace jiha za ta buqaci kyakkyawan nufi da gama kai daga sauran jihohin nan gaba, kamar yadda ta buqata qwarai a da can. gwamnatin Nijeriya, na tabbata, za ta sami goyon baya daga ko ina, wajen gudanar da irin muhimman ayyukan da ta riqe a hannunta.

Mu kam mun yi sa'a qwarai a Arewa, da yake mun sami sukunin gini da inganta sha'anoninmu na mulki, ba tare da mun karya kara

tsakanimmu da al'amuran da ba, ba kuwa da mun watsad da irin tsofaffin al'adunmu kyawawa ba. A bisa wannan kam, lallai ne mu gode wa Sarakuna. Gama kuwa yawancinsu sun gane sha'anin mulkin En'e shi kansa yana canjawa ne, don haka lallai ne su gama kai ainun da majalisunsu, yadda za su yi amfani da wayo da hankalin shugabanin jama'arsu, su zama mataima kansu a cikin mulkin. Babu shakka, auratayyar da aka samu tsakanin abubuwan da a ke da su na gargajiya da Dimukuraxiyya, lallai ne ta zama harsashin kafa gwamnati, wadda ta ke qaqqarfa, mai iya buxuwa.

Gyararren Tsarin Mulkin nan namu, wani mataki ne guda na cim ma niyyar da gwamnatin Ingila ta ke yawan ambatawa. Wato ta miqa wa jama'ar qasashen qarqashin mulkin Ingila sha'aninsu a hannunsu, lokacin da suka ci gaba, har yadda za su iya karvarsa. Irin mutanen da suka je Ingila, za su iya sani mutanen cikin wannan qasa, kuwa, za su riqa duban yadda mu ke ci gaba, tare da tausayi da ganewa. Ana iya cewa Haka nan a game da sauran qasashe, musamman kuwa irin qasashen da ke zumunta da Ingila, don kuwa su kansu ai sun bi irin wannan hanya ne da mu ke bi a yanzu.

Allah Ya ba mu imani, qarfin rai da dagewa bisa gaskiya, domin mu yi amfani da sukunin da aka ba mu, mu yi yadda ke so, wajen sauke nauyace-nauyacen da aka xora mana.[1]

Sardauna ya yi Alqawarin yi wa 'Yan-Adam Aiki

A ranar 1 ga Oktoba, bayan Muqaddashin Gwamna ya gama jawabinsa sai ya danqa wa Sardauna takardar iznin naxa shi Firimiya, sai Sardauna ya miqe, ya yi wannan jawabi:

Ya Mai girma a wurina, wannan lokaci ne na tunani mai zurfi. Mai girma yanzon nan ya xora mini ayyuka, waxanda su ke ba masu qaramin nauyi ba, amma wannan babbar daraja aka ba ni, wadda a ganina, daraja ce aka bai wa dukan mutanen Arewa ta hannuna. Haqiqa, abin da aka yin nan, ya zama kyakkyawan dalili na yin godiya da addu'a.

Saboda haka, a bisa yadda al'adarmu ta ke, ina roqon dukkan waxanda su ke tare da mu a nan, su numfasa, kamar yadda zan numfasa, mu yi wa Allah Maxaukaki godiya, Wanda Ya tsawaita ranmu, har muka ga wannan rana, wanda Ya zave mu, domin ganin

[1] GTK, 13/10/1954 shafi na 4

damarSa, har muka zama cikin waxanda su ke yin wannan gagarumin biki.

Ni kaina, lallai ne in qara yin addu'a, Ubangiji Ya nufe ni da cancantar riqon wannan babban matsayi da aka sanya ni. Ina kuma cikasa addu'ata da xaukar alqawari a fili, cewa na qudure a zuciyata, tun daga yanzu, zam mayar da hakalina dukkansa ga lura da kyautatuwar qasar nan, a bar so gare ni, mahaifata. Tun da yake Allah Ya yi nufi ni ne zan zauna a wannan mafificin mazauni a Jiharmu, na karve shi, tare da matuqar taqawa da qanqan da kai. Na qudure a zuciyata, dukan ayyukan da zan yi, ina Firimiya, zan yi su domin taimakon mutanen Arewa ne, da sauran 'yan-Adam 'yanuwana.

Zuciyata ta yi qarfi qwarai wajen fuskantar waxannan nauyaye-nauyaye da ke kwance gabana, domin abin da ka yi mini, ya Mai girma. Ka yarda a yau, a naxa Ministocin jiha guda tara. Ka yarda a naxa mutane, waxanda su ke kyakkyawan halinsu da ayyukansu sanannu ne ainun, ba a gare ka kaxai ba Mai girma, har ga ko wane talaka.

A cikin Sarakunan jiha, uku sun daxe suna taimakonmu da shawara a cikin majalisa, ba za mu iya rabuwa da su ba. Ina nufin Sir Abubakar, da Malam Ja'afaru, Sarkin Zazzau, da Atoshi Agbumanu, Aku na Wukari. A cikin waxannan muhimman mutane, yau Mai girma, ka yarda ka qara da sunan Alhaji Muhammadu Sanusi, wanda yake a bana ne aka naxa shi Sarkin Kano, ya gaji tsohonsa, karimin Sarkin nan da ya rasu.

Daga cikin Majalisar Wakilai kuwa, har ila yau, Mai girma ya yarda a sake naxa su Ministoci, sanannun abokan aikina, waxanda su ke ba domin su ba, da irin ci gaban da muka yi na shekarun baya, bai samu ba. Su ne Aliyu Makaman Bida, da Yahaya, Madawakin Ilori, da Peter Achimugu, da Alhaji Isa Kaita, da Abba Habib.

A Qarshe, zan yi amfani da wannan kafa da na samu, in gode muku, ya Mai girma, kai da Sir Bryan Sharwood-Smith, saboda kyakkyawar tarbiyyarku, cikin haquri, har kuka kawo Arewa cikin wannan muhimmin muqami da ta ke ciki yau. Ubangiji Ya yi muku albarka, Ya kiyaye ku, tare da mu, mu duka.[1]

A kan hanyarsa ta komawa gida, motoci sun yi jerin gwano wajen rakiyarsa wanda tsawonta zai kai mil guda. Akwai ximbin Jama'a kuma qabilu daban-daban daga sassan wannan jiha da suka yiwa gidansa xango. Waxannan jama'ar wasu sun raka shi bisa babura da

[1] GTK, 13/10/1954 shafi na 4

kekuna, akasarinsu kuwa sun taka sayyadarsu ne. Da suka asa gidansa kuma sai ganguna suka goce da kaxe-kaxe, aka kuma saki tutocin Jam'iyyar NPC iska na ta karkaxa su. Daga bisa ni sai Firimiya ya fito ya yiwa dafifin jama'a jawabi.

Ranar Lahadi 10 ga Oktoban shekarar 1954, gidan Sardauna Firimiyan Arewa, ya cika maqil da dattijai na qabilu iri-iri na Kaduna. Waxansu da qafafunsu suka taka suka tafi, waxansu kuwa bisa kekuna. Mota kuwa sau uku ta ke kwaso jama'a tana kaisu. A nan suka iske Ministoci uku: M. Yahaya, da Alhaji Isa Kaita, da Mr. Peter Achimugu, saboda cuxanya wuri xaya da aka yi, ba nuna wani bambanci, har waxansu suka riqa cewa."Ashe Firimiyan ba dodo bane, abokin kowa ne!" Bayan Sardauna ya gaisa da su, da yi musu jawabi mai kwantar da rai. Ya ce:

Na gode muku, ku duka, saboda xawainiyar da kuka yi a ranar da aka naxa ni. Ina kuwa fata Allah Ya sa wannan sabon matsayi da na samu ya zama mai amfni da albarka ga dukan qasar nan tamu ta Arewa. Idan kuwa ba mai amfani bane, to ni bana qaunar tsawituwarsa.

A cikin jawabinsa, ya bayyana wa dattijan nan ba ya da niyyar shi da dukkan Ministocinsa su nuna wani fifiko ga mutanen Arewa da ke cikin kowace irin qabila. Haka kuma ba zai nuna qyamar kowa ba, don bambancin addini ko bambancin jam'iyyar siyasa. Har ila yau, Sardauna ya yi musu jawabi game da kula da zuwa wajen zave mai zuwan nan. Ya kuma nuna musu aibin rashin zuwa xin. A qarshe dai ya ce:

"Ina yi muku wannan gargaxi ba don neman wani girma ko wata daraja ba ce, sai don amfanin kanku da jama'armu. Burina kuwa shi ne taimakon jama'ar Arewa da tsare mutuncinsu."

A gajerce dai, bayan Sardauna ya gama jawabinsa, sai M. Yahaya Madawakin Ilori, Ministan Lafiya shi kuma ya ci gaba da yi wa jama'a qarin bayani bisa abubuwan da Sardauna ya faxa. Daga shi kuma sai Minista Alhaji Isa Kaita da Minista Peter Achimugu kowannensu ya yi nasa jawabin mai qayatarwa. Duk dattijan nan sun yi na'am da jawabin manyan nan.[1]

[1] GTK, Ta 631, 13/10/1954

Rantsar da Ministoci

Ba tare da vata wani lokaci ba bayan rantsar da shi bisa muqamin Firimiyana Jihar Arewa, sai Sardaunan Sakkwato, Malam Ahmadu Bello ya bayyana sunayen Ministocinsa, kuma dukkan tsoffin Ministoci sun ci gaba da riqe muqamansu, sai dai xan canjin da aka samu game da Sarkin Kano, Alhaji Muhammadu Sanusi.

A lokacin an samu Ministoci guda tara a Jihar Arewa, amma daga baya an qara naxa wasu guda uku bayan an yi zaven Tarayya a watan Disambar shekarar 1959, biyu daga ciki masu ofis, xayan kuma bashi da muqami wato mai bada shawara mara"Portfolio."

Haka nan kuma an bayar da sanarwar malam Muhammad Inuwa Wada Kano Babban Sakataren Jam'iyyar NPC, a matsayin Falmantare Sakatare na Firimiyan Jihar Arewa. Ga sunayen sabbin Ministocin Jihar Arewa da aka rantsar: Sir Abubakar, Minista mara Portfolio; Alhaji Muhammadu Sanusi, shi ma Minista mara Portfolio; Malam Ja'afaru Sarkin Zazzau Minista mara Portfolio; Mr Atoshi Agbomanu na Huxu, Sarkin Wukari, Ministan mara Portfolio; Malam Aliyu Makaman Bida, Ministan Ilimi da Jin daxin Jama'a; Mr Peter S. Achimugu, Ministan Albarkatun Qasa; Malam Isa Kaita, Ministan Ayyuka; Malam Abba Habib, Ministan Masana'antun Cikin Gida; Malam Yahaya, Madawakin Ilori, Ministan Lafiya;

An yi shagulgula iri-iri da samun saqonnin taya murna daga shugabanni na wannan qasa da qetare. Ana daf da naxa Sardauna Firayim Ministan Jihar Arewa, Malam Ahmadu Bello sai Mr. Obafemi Awolowo ya aiko masa da saqon taya shi murna. A cikin wannan saqo ya ce:

"Ina farin cikin tayaka murnar naxin da za a yi maka na Firimiyan Jihar Arewa. A wannan sabon falle na siyasa da ke tafe, na aiko maka da jama'arka kyakkyawar niyyar Jihar Yamma, da mutanenta da ni kaina. Idan aka samu aiki tuquru da nuna gaskiya, da sadaukar da kai daga gareka da cusa xa'a a jama'ar ka, na tabbata za mu kai ga nasara, da taimakon Ubangiji.

Ina fata Allah Ya qara mana imani, qarfin zuciya, da qarfin halin yin amfani da wannan damar da muka samu don ciyar da qasar gaba ta hanyar nuna sanin ya kamata wajen sauke nauyin da aka xora mana."[1]

Aikin Hajji

A shekarar 1955 Ahmadu Bello ya fara zuwa aikin Hajji. Tun daga wannan shekara bai yi fashin aikin Hajj da Umra ba, har ya zuwa qarshen rayuwarsa. A shekarar 1959, Arewa ta samu Mulkin Kai. A wannan shekara ce kuma

[1] GTK 7/10/1957, shafi na 3

Sarauniyar Ingila ta karramashi da lambar girma mai daraja ta *Knight of the British Empire* (KBE) daga nan ya zama "Sir" Ahmadu Bello.

A shekarar 1960, Nijeriya ta samu Mulkin Kai. A wannan shekara ce kuma ya zama Mataimakin Shugaban qungiyar Musulmin duniya wato *World Muslim Leaque*. A shekarar 1963, Sir Ahmadu Bello ya zama Shugaban Jami'ar da ya kafa na farko,"Ahmadu Bello University Zaria." Gamji Mazan Qwarai, ya yi shahada ran 15 ga watan Janairu na shekarar 1966, a wani juyin mulkin sojoji, a gidansa da ke Kaduna.

Wannan Gidan Sardauna, sai ya zama wata cibiyar binciken Tarihi da adana kayan tarihi babba wato *Arewa House* a garin Kaduna. Wannan gidan tarihi sai bunqasa yake yi sosai.

Ziyarar Matar Sardauna

A shekarar 1995, sai Farfesa Abdullahi Mahdi Daraktan Arewa House ya ce mu yi shirin qarvar Babbar Baquwa, a wannan gida. Hajiya Amina Gwaggon Kano, matar Sir Ahmadu Bello za ta kawo ziyara gidanta bayan cika shekaru talatin cur, da ganin tashin hankalin 15 ga watan Janairu na shekarar 1966. A wannan rana ce ta yi rashin mijinta da kishiyarta Hajiya Hafsatu Gwaggon Qurya. gwamnatin Jihar Sakkwato ce ta shirya wannan muhimmiyar ziyara.

Ta zo wannan gida *Arewa House* da Basmallah da ayarinta na 'ya 'ya da jikoki da dangi tare da muqar-raban gwamnatin jiha. Daraktan cibiya da ayarinsa ya qarvesu da lale da marhabin. Wannan amintacciyar baiwar Allah, ta zo ta nuna qarfin imani da ba da wuya ga Hukumcin Allah Mai girma. Aka zaga da ita duk xakunnan gida, ita kuma tana duba su tana du'a'i ga Allah Ya jiqan mijinta da *'yar'uwa*rta da sauran waxanda suka yi shahada a wannan rana, Allah Ya jiqansu Ya Rahamshesu, amin.

Sir Ahmadu Bello yana da mata uku: Hajiya Hafsatu Gwaggon Qurya da Hajiya Amina Gwaggon Kano da Hajiya Fatima Gwaggo Javvo. Yana kuma da ya'ya uku: A'i, da Inno (Bici), da Lubabatu. Jikokinsa kuma sun haxa da: Asma'u, da Hadiza (Hajiyayye) da Abdulqadir, da Fatima (Balaraba), da Safiya, da Hadiza, da Hassan da Husani, da Maryam (Mamu), da Aisha, da Hafsatu da Ahmadu Bello.

Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato ya saha waqoqi iri-iri daga mawaqan Hausa na qasashe daban-daban. Saboda ayyukan da ya yi wa Arewa ne ya sa ake cewa har qasa ta naxe ana tuna shi. A cikin jerin gwanon waqoqin da aka yi wa Sardauna, akwai ta Alhaji Muhammadu Lambo Sakkwato, wadda ita ma cike take da ma'anoni.

Waqar Firimiya

Bismillahi Zan Yi Waqar Karimi,
Bello, Balarabe Uban Jam'iyyar Arewa.

Na Gode Ma Bello Gogarima Gamji xan qwarai,
Kyawon Hali Da Tsai Da Adalci Ya Fi Kowa.

Tun Da Ya Zam Kana Da Adalcin Tsai Da Gaskiya,
Gwamma Da Kai Yi Shugaban Jam'iyyar Arewa.

Alhaji Bello Ahmadu, Sir Sardauna Sakkwato,
Kyauta Garai Kamar Ruwa Kullum Mai Zubowa.

Xangarama Maganin Ruwa, Tamraron Tsakar Dare,
Ba Domin Kai Ba, Da Ruwa Sun Canye Arewa.

Ga Babban Tudun Jigawar Lillahi Sarki,
Dutse Ko Wa Kara Da Kai Baki Na Fashewa,

Ga Mai Arziki Kamar Mai, Mai Nashe Fili,
Duk Damshin Arzikinsa Ya Na Nashe Arewa.

Ga Gamzaki Mai Fita Da Subahin Uban Zagi,
Ga Baban Kadiri Uban Zarumi Har Kabawa.

Baban Sallama Uban Sarkin Fada Sarki,
Zamnawarka Lafiya Lau Lardin Arewa.

Dogon Shugaban xiya Baban xan Arago,
Mulum xai Bakin Mutum Dubu Jan Zakin Arewa.

Al'amarinka Na Da Girma Gun Jalla Sarki,
Yaro Duk Ba Shi Taka, Babba Ma Bai Iyawa.

Yaro Ko Shina Gaban Matatai Gidanai,
Tace Mishi Zai Kamarka Yai Shakkar Bai Iyawa.

Babban Tambari Uban Gangumma Da Taushi,
Ga Babban Shugaban, Uban Jam'iyyar Arewa.

Allah Maganin Abokin Gabarka xan qwarai,
In Ka Ga Bai Mace Ba, Sai Ko Ya Kasa Kowa.

Bar Maqiyanka Nan Ga Allah Shi Zai Isamma,
Zurum Ma, Ta Isamma Mai Son A.G. Arewa.

Da Mai Jada Shi Ayau, Shi Ne Zai Ci Baya,
A Kashe Kansa duniya Sai Ta Hori Wawa.

Ba Mai Ja Shi, Cikin qarninai Da Yan'uwa,
Tun Da Ya Samu Taimakon Allah Mai Iyawa.

Ahmadu Bello xabi'ar Manya Na Ainahi,
Kwai Yi Hali Irinka Aljanna Zai Shigewa.

Ahmadu Bello Bai Fushi Sai Wasa Da Dariya,
Ko Ka So Jiye Ma Gogarman Ba Shi Ji Ma,
In Kai Sharri Ka Kan Yi, Alhairi Zai Mayarwa.

Ko Ka So Barin Siyasa, Ba Za Mu Yarda Ba,
Ran Da Ka Bar Mu duniya Ta Ruxe Arewa.

Tun Da Fa Wanga Zamani Ne, Mai Juya Hali,
Kammalar Arzikinmu Kai Ne Leader Arewa.

Tun Da Ka San Tabara Sarki Ke Taimaka Ma,
Gara Ka Hanqure Ka Ja Jam'iyyar Arewa.

Wa Ke Kokowa Da Mai qarfi Ukku Shi Kaxai,
Sai Ko Sardauna Raqumi Dangi Mai Arewa.

Bar Yaba qokarin Kare, Mai Wasa Da Kura,
Kan Dai A Jinjima Kaxan, Nama Zai Zamowa.

Wayo Na Wurin Dila Ba Ko xan Kaxan Ba,
Ka Ga Shi Ya Ci Arzikin Jam'iyyar Arewa.

Sai Dai Anniya Da Tuban Tsohon Muzuru,
Kaza In Ta Yi qyanqyasa 'Ya'yan Zai Kashewa.

Mu Roqi Tabara Tun Dashi Ne Mai Gyara Komi,
Shi qara Tsare Premier Mai Lardin Arewa.

Ban Gajiya Da Gai Da Kai, Don Ko Ka Fi 'Yan'uba,
Adalci Da Son Mutanen Lardin Arewa.

Tilas Ne Yabon Gwani Tun Ba xan'uwanka Ba,
Gamji Farar Zumar Da Kowa Ke xanxanawa.

Dutse Ba Ka Fargaba Baban Ali Odale,
Baban Mamman Bakura, Mai Jagorar Arewa.

Inda Dai Ana Macewa Sannan A Komo,
Na Tuna Isa Dutse, Mai qamnar Sakkwatawa.

Yaro In Kana Da Kyawo qara Da Wanka,
In Ka Gama Da Sabulu Kyawo Na Fitowa.

Duka Ba Shi Kada Mai qarfi Kan Masaba,
A Kama Bugu, A Kwan Bugu Kan Nan Bai

Nutsewa.

A Yini Ruwa A Kwan Ruwa, Dutse Bai Kula Ba,
Ga Zane Nan Ga Zabuwa Don Ba Ya Dushewa.

Babba Ka Ci, Ka Sha, Ka Aikin qarfi Da Girma,
Shi Ka Tsare Faxan Da Yaro Ba Ka Iyawa.

Masu Abinsu Dole Kai Ke Ci Da Rana,
Kwats Tsare Gaskiyarsa, Mulkinai Na Daxewa.

Ahmadu Bello Adali, Yayan Shehu Cigari,
Babba, Uban Marafa Mai qaunar Arewa.

Ahmadu Bello Gamji Mai Siffar Larabawa,
Shi Da Sa'udi Gun Muruwa Ba Rarrabewa.

Ahmadu Bello Wan Maza Kalacinka Girma,
Al'amari Idan Na Girma Ne, Bai Gazawa.

Ahmadu Bello Mai Jiran Mai Amsa Shi Amsa,
Kyauta Ga Bello, Gamji Sai Kwana Ke Hanawa.

Ahmadu Bello, Tun Shina Yaro Ba Shi Wargi,
Kowace Safiya Da Himmatai Zai Fitowa.

Kowacce Zai qi Wanda Allah Yab Baiwa Girma,
Tun Daga duniya Mutuncinai Ke Zubewa.

Tun Da Abinga Naka Baiwa Ce Rabbu Yai Yima,
Mai Nukura Da Taka, Shi Haushi Zai Kashewa.

Bello Fari, Balaraben Ibrahim Dasuqi,
Gamda'aren Shatima Gwamnan Arewa.

Bello Bakadiren Makaman Bida Da Musa,
Gashash Mai Riqon qasashen Lardin Arewa.

Bello Giyen Turaki Ali, Mai Zazzagawa,
Bello Giyen Garandi Kadi, Lardin Arewa.

Bello Uban Minista Shehu Sarki A Maska,
Da Nasiru, Malamin Shari'ar Lardin Arewa.

Bello Uban Bashiru Wamban Daura Karimi,
Bello Bayajidda A Daura Zakin Arewa.

Bello Fari qane Ga Suldani Garba Sarki,
Bello Zumun Amiru Ado Zakin Kanawa.

Ahmadu Bello Sabulu Ne, Mai Wanke Hausa,
Bello Farin Cikin Mutanen Lardin Arewa.

Mai Son xanqwarai Shi Haifi Na Kirki Guda xai,
Bello Muwafaqar Mutanen Lardin Arewa.

Ba Himi Garan Ba, Ni Ko Ba Jahili Ba,
Amma Fa, Abinda Nis Sani Shi Kam Zam
Bayyanawa.

Don Maganar Kano, Abinai Ne Ya Yi Gyara,
Don Shi Kashe Faxin Kano Dai A Bai Takawa.

Ya Bugi Gaskiya,a Daxa Du qarya Ta Vuya,
Domin Jama'a Su Daina Zargi Lardin Kanawa.

Sai Amvata Zuciyar Sa, Kan Kai Ga Romo,
Kan Lamari Ya Yamutse Gyara Za A Sawa.

Ahmadu Ya Yi Alkawal qullin Zamaninai,
Maulkin Kano Shina Ga Hannun Abbasiyawa.

Mu Roqi Tabara Jalla Allah Mai Gyara Komi,
Shi qare Tsare Premier Mai Lardin Arewa.

Ahmadu Bello Wanda Ya Ce Duk Za Shi Ja Ma,
Jefa Shi Baro Can Shi Zam Magudanci Bawan Nufawa.

Gamji Zuma Marar Gami, In An Nemi Zaqi,
Ga Bindigar Wuta Cikin Da Mugunta Gun Mai Turawa.

Tun Da Maso Jalla Ka Ke, Sai Mu Tsare Sai Mu Fake,
Wanda Ya Ce Nasa Ka Ke, Im Bai Yi Gaskiya Ba,
Mu Taru Mu Mai Da Shi Ruwan Gebe Mai Wucewa.

Ya Jama'a Duk Ku Jiya, Ko Wagga Yau Yagga Jiya,
Sai Mu Yi Mai Ban Gajiya, Don Daji Ya Ratso,
Ya Yi Karo Da Manya Manyan Zaki Da Giwa.

Ahmadu Sarkin Jama'a, Mai Tsare Haqqin Shari'a,
Don Haka In An quri'a Shi Ne Zai Ci Kowa,
Ba Wani Mai Nufin Tsayawa In Zai Tsayawa.
Gamji Mutane Jama'a Kai Ka Gudun Tsere Sa'a,
Ko A Tsaya A Yi quri'a, Ko Hali Na Girma,
Ahmadu Bello Wanga Zamani Ka Fi Kowa.

Kai Aka Ba, Kai Ka Iya, Kai Ke Faxi Du A Jiya,
Ka Isa Manyan duniya, Du An Ko Sakkam Ma,
Abin Da Kace, A Baiwa Afirka Ba Hanawa.

Ahmadu Babbar Magana, Ka Kashe Babbar Fitina,

Masu Awo Sun La'ana, Sun Auno La'ari,
Yanzu Idan Ka Ce Awo Noma Za Su Cewa.

Sai Mu Yi Alhamdu Duka, Tun Da Magabtammu Duka,
Su Duka Mun Kai Su xaka, Sun Koma Akurki,
Kowanen Babu Mai Shigowa Ba Mai Fitowa.

Bar Su Da Allah Shi Tsare, Sun Hak Sharri Shi Tsare,
Ko Da Hama Ko Da Dare, Dukan Kan Masaba.
Masu Bugunta, Yau Da Kullum Su Ke Gazawa.

Tun Da Mutane Ka Faxi, Ka Fi Zuma Ka Fi Maxi,
Ba Ka Aboki Ga Haxi, Don Ka Gadi Girma,
Ka Isa Shugaban Mutanen Lardin Arewa.

Ahmadu Ya Zam Zakara, Wanga Na Babbar Faka,
Masu Haqo Sun Makara, Har Ya Faxa qumci,
Sun Yi Dako-Dako, Suna Dako Bai Fitowa.

Allah Kaxai Ka Iya, Kai Ka Gava Ka Yi Karaya,
Masu Gudu Duk Su Tsaya, Iko Sai Ta'ala,
Jalla Jalali Mai Haxawa Mai Rarrabawa.

Allah Sarkin Rahama, Kai Ka Iya Maxacci Da Zuma,
Mai Fitina Du Shi Ruma, Mu Mun Samu Rana,
Yanzu Daxa Shanya Gari Ba Mai Zubarwa,
Alhamdu-Lillahi, Rabbbil Alamina.

"KASIDA"

Bayan Gaisuwa Da Yarda Babban Ubangida,
Ga Wata 'Yar qasida Na Zo Don In Yaba Ka.

Yau Falalar Mujaddadi Ka Same Ta Mun Gani,

Don Kuwa duniyar Duk An Amsa Kiranka,

Halin Bello Ko Guda xai Bai Kuskure Ba.
Gaman Haka Nij Ji, Tun Da Kunne Ya Girmi Kaka.
In Ka Tashi Shawara, Sai Ka Tara 'Yan'uwa.
A Kan Hakanan Ubangiji Allah Ke Tsare Ka.

Gamji Haliu Mujaddadi Shi Jabbaru Yai Yi Mai,
Ka qishi Ka So Shi, Ba Shi Nuna Ma Ba Shi Sonka.

Gamji Da Kake Yin Horo Ga 'Yan'uwa,
Sai Wanda Ka Son Shi qulla Zumunci Ke Gudunka.

Kai Maqiyanka Anka Samu, Sun Sallama Ma,
Don Kuwa Sun Ga Babu Mai Adalci Irinka.

Babban Wabili Guda xai, Mai qwadda Karkara,
Gamji Ruwan Kashin Fari Shina Har Ga Kaka.

Tun Da Nufinka Duk, Na Alherina Ga Kowa,
Jalla Jalali, Rabbana Zai Ja Zamaninka.

Alherin Da Jalla Ke Ba Bayinsa Kullum,
Shi Ba Ka, Shi Koma Ba Ka, Don Kyawon Aniyarka.

Ni Roqqo Ni Kai Ga Allah Sarki Ta'ala,
In Ga xiya Maza Da Mata Sun Kewayeka.

Sun Yi Dubu, Kuna Ta Wasar Jika Da Kaka,
Amin Amin !!![1]

[1] Wa}ar Firimiya Sir Ahmadu Bello Daga Alhaji Buhari Lambo Sakkwato. GTK, 30 ga Yuli 1964, p. 6

Ayyukan Ahmadu Bello

Firimiya Sir Ahmadu Bello ya yiwa Arewa ayyuka muhimmai kafin ya yi shahada. Ya yi katafaren ayyuka sun taimakawa qasarsa da jama'arsa wajen ciyar da Arewa gaba, suka kuma xora ta abisa sahun sauran Jihohi. Duk da cewa an bar jihar Arewa a baya amma a cikin 'yan sekaru bakwai kacal da shigarta Siyasa sai ga shi ta yi hovvasa wajen nuna ita jiha ce mai mabambanciya da banmamaki. Jama'a sun shaida yacika kusan duk alqawurran da ya xauka a duk matsayin shugabancin da ya riqe. Saboda haka ne ko da Sardauna ya zama Firimiyan Arewa a shekarar 1954, sai ya zama wani gwauron giwa kuma katafaren xan-siyasa-qifaxi a wajen gwagwarmayar fito da Arewa daga qangin da ta samu kanta ciki. Wannan nasarar da Sir Ahmadu Bello ya samu a kan wannan batu ya sa ya zama, shugaba kuma maginin al'umma wanda har qasa ta naxe ba za a manta da shi ba. Ilimi, shi ne mabuxin arziqi don haka ya yi hovvasa wajen gina makarantu da Jami'ar da aka raxawa sunan sa. Ita wannan mashahuriyar makaranta tana daga cikin muhimman ayyuka da ya yi. A zamaninsa Makarantar Koyon Mulki aka fara buxewa.

Bikin Buxe Makarantar Koyon Mulki

Sabuwar Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya ta ga dubban mutane ran 24 ga Afrilu, ranar da gwamnan Nijeriya Sir John Macpherson, ya buxe ta a gaban muhimman mutane na jihohin Nijeriya uku – Arewa, Gabas da Yamma. Ko da yake an kwana ruwa, an tashi da shi a safiyar wannan rana, duk da haka a cikin ruwan mutane dubbai, waxansu a kekuna, waxansu a motoci, waxansu ma a qasa, suka yi ta tafiya wurin. Kafin qarfe takwas da rabi na safe, babu sauran wurin zama, sai ko mutum ya tsaya. Da yake waje a jiqe yake, a wani babban xaki na makarantar aka cunkusa mutane damfam. Ga Sarakuna, ga Turawa, ga Ministocin jiha, ga Dr. Nnamdi Azikiwe – ministan mulkin En'e a Jihar Gabas, ga Mr. Obafemi Awolowo – Ministan Mulkin En'e a Jihar Yamma, ga Oba Adele Sarkin Ikko da hakimansa. Ga wakilan Majalisar Jihar Arewa da yawa. Ga sauran mutane masu yawan gaske. A lokacin da Gwamna ya iso makarantar, babu shakka, babu sauran wurin zama inda mutum zai ji daxi. An cika Babban Gwamna ya iso qarfe tara ba minti biyar na safe, tare da uwargidansa, da sakatarensa, da Sir Bryan Sharwood - SmithLeftana Gwamna na Jihar Arewa da uwargidansa. Sardauna da babban Baturen makarantar suka tarye shi. Bataliyar soja da aka jera suka gaishe shi, sa'an nan yakewaya su. Ya sake komawa kan dakalin da aka yi masa ya tsaya, bataliya suka sake gaishe shi. Suka yi taken Sarauniyar Ingila, jama'a duk na tsaye. Daga nan Sardauna na gaba, tare da babban Baturen makaranta, Mr. Cory, suka rako manyan baqin xakin da aka taru.

Bayan su Gwamna sun zauna a kujerunsu, sai Mr. Cory da M. Isa Wali suka miqe. Mr. Cory na jawabi da Turanci, M. Isa na fassarawa da Hausa. Kowa na da abin qara girman murya gabansa. Mr. Cory na qarewa, sai ya roqi Minista

Sardauna ya yi nasa. Sardauna ya yi dogon jawabi, shi kuma ya roqi Gwamna a buxe wannan makaranta. Buxewar, ba wata qofa Gwamna ya buxe ba. A'a, wani allo ne na qarfe aka kafa jikin bango. Jikin allon an rubuta Gwamna ya buxe Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya ranar 24 ga Afrilu, 1954. Kafin Gwamna ya buxe allon, ya yi jawabi, Jawabin nan ya bai wa mutane sha'awa ainun.

Daga nan sai Gwamna da sauran 'yan rakiyarsa suka fita, jama'a duk kowa yana zaune wurinsa. A lokacin ne Mr. Cory ya ce kada mutane su manta da zuwa wurin hira da la'asar a nan makaranta. Soja suka daxa gai da Gwamna, sa'an nan ya shiga mota ya nufi masaukinsa, wato jirginsa. Amma da rana Gwamna ya sake komawa makarantar. Sardauna da Mr. Cory suka tarye shi a qofa, suka kewaya da shi azuzuwanta goma sha-xaya (11) da xakunan yara.

Kafin qarfe huxu na maraice, babban filin nan na tsakiyar makarantar ya cika da mutane. "Babu irin mutumin da babu na kirki, Sardauna na tsaye, yana yi wa baqin nan maraba. Turawa, da Sarakuna, da Ma'aikata, 'yan kasuwa da sauran mutanen da suka kamata, sun haxu a wurin. Lemo, taba, goro, biskin, da sauran kayan lashe-lashe, sai da suka yi saura.

Wurin hiran nan, ya yi kyaun shiri. Kowane tebur ga mutane ana ta taxi, ana kurve-kurve da taune-taune. Waxannan su tashi su koma can, waxancan su koma nan, ana jujjuyawa, yadda mutane za su riqa gaisawa da juna. Kowa na cikin farin ciki da annashuwa. Jama'a suka yi wandaqa da warisa. Shugaban Makarantar kuwa baki har kunne. Idan ka dubi fuskar wannan mutum, ba sai an faxa maka ba, za ka tabbata ya sami biyan buqata. Haka kuma Dr. Azikiwe da Mr. Awolowo. Dukansu wannan tsari ya ba su sha'awa da gasken gaske.

Da almuru kuwa taron da aka yi, a gidan Razdan ne. Nan ma Turawa da Baqar Fata sun haxu. Abin kam ya yi matuqar kyau. Kowa ya gaisa da Gwamna. Mutum na shigowa, sai Wakilin Razdan, domin shi Razdan na Zariya, Mr. C.V. Williams ya tafi lifi, ya sada shi da Gwamna da Uwargidansa su gaisa, sa'an nan mutum ya wuce, boyi-boyi su kawo masa irin abin da yace yana son sha ko ci. Kai, Zariya ba za ta manta da ranan nan ba."[1] Ai irin wannan wandaqar da warisar da aka yi sai wanda ya gani.

Bayan Mr. R. M.C. Cory, shugaban Makarantar Koyon Aikin Mulki ya zauna, sai kuma Mai girma M. Ahmadu, Ministan Mulkin En'e na Jihar Arewa ya tashi ya yi nasa jawabi, kafin ya roqi Gwamna ya buxe wannan makaranta. Sardauna yana rataye da lambar C.B.E., wadda gwamnan Nijeriya ya liqa masa a Kaduna ranar Jumma'a. Ya ce:

[1] GTK 24/4/1954

Mai girma, gwamnan Nijeriya mu duk jama'ar Jihar Arewa, muna matuqar farin ciki da ka sami dama ka zo, saboda buxe Makarantar Koyon Aikin Mulki. Zuwan nan naka ya nuna a fili irin sha'awa da muhimmancin da ka xora bisa koyar da aikin mulkin En'e. Muna kuma farin ciki da ganin Leftana gwamnanmu wanda muka sani shekara da shekaru, wanda kuma ya yi matuqar aiki domin ciyar da sha'anin mulki gaba a Jihar Arewa. Abin kuma murna ne a gare mu, da muka ga Sarakuna da yawa, 'yan Majalisar Ministoci, Majalisar Zartaswa da kuma 'yan Majalisar Wakilai, waxanda da yawa cikinsu, bayan aikin su mai tsanani, sun sami lokacin zuwa, daga kuma nesa qwarai, domin wannan biki.

Haka kuma muna yi wa manyan Ministocin sauran jihohi maraba. Muna farin ciki da nuna musu irin xan abin da mu ke yi game da sha'anin mulkin En'e a Arewa. Sarkin Ikko, Oba, ba baqo ba ne a Arewa, domin yana ma aiki a Kano ne aka naxa shi wannan matsayi nasa na yanzu. Mun yi murna da sake ganinsa.

Makarantar koyon aikin mulki da Gwamna zai buxe yau, a da sunanta Makarantar Koyon Aikin Akawu Akawu. Yanzu ba masunan kaxai ya canja ba, an sake gine-gine sabbi duka. Farkon shekarar bara aka fara aikin, ina kuwa farin ciki da godewa fidaburdi, saboda kyakkyawan aikin da suka yi da sauri da tsimin da suka yi wajen qare wannan aiki.

Qare wannan gini da sauri ya ba mu damar yaxa fannonin da za a iya koyo. A da abin da a ke koya wa almajirai, su wajen 120 ne ko wace shekara, aikin akawu da aikin Baitulmalin En'e. A bisa waxannan za a qara fannoni masu yawa yanzu, kuma almajirai za su kai wajen 180. Manyan ma'aikatan En'e za su iya samun diploma wajen aikin Baitulmali. Wannan babban muhalli ne, ana kuwa fatar nan gaba samun diploma xin nan ya zamana shi ne mabuxin qofar samun babban ci gaba wajen aikin Baitulmali.

Bayan waxannan kuma, akwai Kwas da dama iri-iri na koyon aikin mulki, za a shirya wa Hakimai irin nasu, malaman Hakimai da irin nasu, da duk sauran masu irin wannan matsayi a duka Jihar nan. Sa'an nan kuma tsofaffin ma'aikatan En'e da suka yi shekara 10 zuwa 15 a aiki a hedkwatar En'e za a shirya musu irin nasu Kwas mai zurfi. 'yan Majalisar En'e an shirya musu irin Kwas xin da za su yi.

Sa'an nan kuma mataimakan Di'o masu rangadi za su riqa yin bita, domin su san irin abubuwan da a ke koyarwa a wannan makaranta. Sarakuna ma an shirya musu nasu Kwas wanda za su riqa yi a Kaduna ko wace shekara. Nan gaba ana iya qara waxansu Kwas idan an ga

hali ya yi. Wato ke nan tun daga qaramin akawu har bisa wanda yake kan En'e duk kowa an shirya masa yadda zai qaru da aikinsa. Ina qara qarfafawa, cewa yawancin irin duk koyon da za a yi nan makarantar, za a yi shi ta wajen aikatawa ne. Ko da yake akwai koyo a takarda, amma duk da haka babban maqasudi, shi ne a koya wa mutum, ta aikawa, yadda zai tafiyar da aikinsa na En'e dai-dai.

A nan Arewa, muna fahari da hanyan nan tamu ta mulkin En'e. An gina ta bisa harsashi na al'ada mai qwari. Yanzu kuma ana qara inganta ta da sauri, saboda wannan ne muna buqatar ma'aikata qwararru da za su tafiyar da ayyukansu yadda a ke buqata, a bisa hanya managarciya ta zamani. Mun yi sa'a qwarai a Arewa, da muka sami mutane da yawa gogaggu cikin sha'anin mulkin En'e. Da yawa cikinsu an haife su kuma sun girma a cikin sha'anin ne, kuma da yawa sun daxe suna wannan aikin. A cikinsu akwai samarin ma'aikatan En'e da suka yarda da wannan hanya ta En'e.

Ina fata dukan almajiran da za su zo wannan makaranta su amfana da irin taimakon da shugaban makarantar da mataima kansa za su iya ba su, taimakon da na tabbata mai kyau ne. Ina fata, almajiran nan, ko yara ne da suka fito makaranta, ko tsofaffin ma'aikatan En'e ne, za su yi aiki mai tsanani, bisa ga wannan dama da suka samu don su qara inganta sha'anin mulkinsu. Ana iya bai wa almajiri ilimin da ya kamata a nan, amma aikatawa bisa adalci da gaskiya ya dangana ga shi mutum kansa. Don haka ina fata idan almajirai sun gama koyonsu, za su ci gaba da aikin nan mai tsanani a En'ensu.

Ina son in rufe maganata da qara gode wa dukan waxannan da suka sami damar halaratar wannan biki a yau."[1] *Daga nan sai Sardauna ya roqi Mai girma gwamnan Nijeriya ya tashi ya yi jawabi, sa'an nan ya buxe makarantar. Amma kafin Babban Baqon yayi jawabinsa sai da shugaban Makarantar ya gabatar da nasa.*

Jawabin Shugaban Makaranta

Mr. R.M.C. Cory sai ya miqe ya yi jawabi, inda ya ce: *"Mai girma gwamnan Nijeriya. Babbar falala ce gare ni da farin ciki a yau, in bayyana marabarmu, ni da sauran abokan aikina, ga manyan mutanen nan da suka taru a nan, don su ga wannan shagali na buxe muhallin nan na koyon sha'anin mulki. Babu lokacin da zam ba da bayanin yadda muhallin nan ya kawo har ga yadda yake yanzu, filla filla, to, amma ana iya tunawa cewa am buxe makarantan nan ta Koyon Aikin Akawu a watan Afrilu ne na shekarar 1946, don ba da horo ga akawunan En'e*

[1] GTK ta 607, 28/4/1954

En'e. A lokacin da aka buxe almajirai 36 ne. A cikin shekarun nan takwas na wannan makaranta, an karvi almajirai kusan 600 a cikinta.

A yau ana horar da almajirai 233 a fannoni daban-daban a cikin wannan muhalli. Bayan sun gama koyon nan nasu, da yawa daga cikinsu za su kama ayyuka, ko kuma su ci gaba da ayyukansu, a ma'aikatun gwamnati da na En'e – En'e, waxansu tare da kantuna. Ci gaban nan da aka samu, ga tsammanina, saboda manyan abubuwa guda uku ne, su ne:

Da farko, sha'awan nan matuqa da kuma taimako da masu iko suka nuna su ne gwamnati da En'e – En'e, ga ma tabbatacciyar shaida nan sun nuna wajen halartar buxe gine-ginen nan. Na biyu, shi ne biyayyan nan da kuma qwazo da ma'aikatan wurin nan suka nuna. Kashi 80 cikin 100 na masu koyarwa duka 'yan qasar nan ne, dukansu kuwa tsofaffin almajirai ne na makarantan nan ta koyon aikin akawu, waxanda aka zave su da kyau saboda qwazonsu da gwanintarsu. Saboda su kansu sun bi ta cikin surquqiyan nan, ana iya xauka kan cewa su ne mutanen da suka fi cancanta su bi da saura ta cikin wannan surquqiya. Ina so in yi amfani da wannan dama in nuna godiyata, a cikin jama'a, ga ma'aikatun nan da kuma En'en nan da suka gabatar da buqatun Jihar nan da farko, ta barin ma'aikatansu da suka yi don su yi aiki a wannan muhalli.

Abu na uku da ya jawo wannan ci gaba, shi ne niyyar haxa kan nan da muka samu daga yawancin almajirai. Galibinsu sun gane muhimmancin aikinsu, sun kuwa nuna kyakkyawar buqata ga yin matuqar qoqarinsu. A yau fannin nan na aikin akawu yana samar da ma'aikata ga ma'aikatun gwamnati da na En'e, amma a yanzu yawan buqatar da a ke da ita ya shige yawan abin da a ke iya samu da gaske.

Alhakkin muhallin nan na Koyon Sha'anin Mulki yana cikin ayyukan minista na mulkin En'e ne, wanda ko yaushe ya kan nuna matuqar sha'awarsa wajen ci gaban muhallin nan da kyautatuwarsa. Sabo da haka ina farin cikin samun darajar kiran Mai girma Ahmadu Sardaunan Sakkwato, ministan mulkin En'e da raya zaman jama'a na Jihar Arewa ya yi muku jawabi.[1]

Zik da Awo Sun Kai Ziyara

Ranar bukin buxe mashahuriyar Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya, manyan baqin da suka zo wannan shagali sun ga abubuwan ci gaba masu yawa a wannan Jiha. A wannan rana 24 ga Afrilun shekarar 1954, da rana sai M. Ibrahim

[1] GTK ta 607, 28/4/1954, shafi na 8

Dasuqi, Sakataren Minista Sardauna ya zo Kamfanin Gaskiya tare da manyan baqin Jihar Arewa, Dr. Nnamdi Azikiwe, Ministan En'e na Jihar Gabas da Mr. Obafemi Awolowo, Ministan En'e na Jihar Yamma. Wakilin Janar Manaja, Mr. Salt da Alhaji Abubakar Imam, da M. Abdulqadir Makama Editor-in-Chief, da M. Abubakar Tunau, Editor na Gaskiya, da M. Cindo, Editor na Citizen suka tarye su a qofa, suka shiga kewayawa da su wuri wuri.

A wannan lokaci sai wakilin Gaskiya ya tambayi Dr. Azikiwe ra'ayinsa game da Jihar Arewa yanzu. Dr. Azikiwe sai ya ce, Arewa ta sake masa a yadda ya santa. Yanzu kam tana gaba da gaske. Ya ce yana ganin Arewa fa ita ta ke Jan Ragamar Nijeriya. A game da Kamfanin Gaskiya kuwa sai ya ce,"In dai ba maxaba ar gwamnatin Nijeriya ba, kuna gaba da sauran maxaba'o'i.[1]

Amma da aka tambayi ra'ayin Mr. Awolowo, wataqila ya gune ne sai ya ce ya yi sha'awar jerin basukur ne na Ma'aikatan Gaskiya. Ya kuma matsa kusa ya dubi kekuna tantsai.[2]

Ko da yake waxannan manyan baqi sun nuna sha'awar koyon Hausa amma Zik da bakinsa ya ce, "Da na je Kano gidan Sarki, Razdan ne ya riqa yi mini tafinta. Ni ina magana da Turanci, yana fassarawa Sarki da Hausa. Na ji nauyin wannan abu. Na cewa Sarkin Kano lallai zan koyi Hausa da Hausa za mu yi magana."[3]

A lokacin da waxannan manyan baqi suka kawo ziyara ana kuma kewaya wa da su wuri-wuri sai ga Sarkin Lafiya ya iso. Aka haxu, ana tafe M. Tunau yana ta xaukar hotunansu. Kowane injin aka je, sai an tsaya an yi musu bayani. In suna da tambayoyi su yi, a basu amsa. Kafin a qare sai Atta na Igbirra Alhaji Ibrahim shi ma ya iso. Gaba xaya fa aka yi ta yi, sai da aka yi misalin sa'a guda, sa'an nan aka rako su qofa aka yi sallama.[4]

Kamfanin Gaskiya sananne ne a Nijeriya saboda yana xaya daga cikin manyan kamfanoni da ke da kayayyakin aiki da gine-gine irin na zamani. Saboda haka ne yake samun ziyarar manyan mutane 'yan Qasa da Turawa akai-akai. Kamar yadda Dr. Azikiwe ya ce ne wannan maxaba a na gaba da sauran maxaba'o'i a Nijeriya!

Kwas na Sarakuna

Tun da aka buxe wannan mashahuriyar makaranta Hakimai da Alqalai ke zuwa yin Kwas wajen aikin mulkin En'e da sauran harkokin mulki da shari'a

---

1 *Ibid.*

2 *Ibid*

3 GTK ta 607, 28/4/1954, shafi na 8

4 *Ibid*.

daban-daban. Ana yin haka ne saboda Sarakuna su fahimci zamani da alqiblar da gwamnatin Jihar Arewa ta fuskanta domin a sami dai-daita wajen mulki da yin ayyukan raya qasa da jin daxin jama'a. Ita wannan gwamnati ta duqufa bil haqqi da gaskiya wajen ciyar da Arewa gaba. Saboda haka ne ta tsaya tsayin daka taga Sarakuna sun dulmuya ka'in da na'in a harkokin mulki. Saboda ta fahimci tasirin mulkin En'e a Arewa da kuma muhimmiyar gudunmawar da Sarakuna za su bayar wajen gina Sabuwar Arewa.

Sarakuna da mulkin En'e nada muhimmanci sosai saboda haka ne gwamnatin Jiha ta naxa Ministan Mulkin En'e da Jin daxin Jama'a. Sardauna Ahmadu Bello ne ya fara riqe wannan muqami, Hukumarsa kuma ta shimfixa ayyuka masu yawan gaske da suka taimaka gaya wajen ciyar da Arewa gaba. Wannan Hukuma tana da qarfi sosai ko da M. Abdullahi MaiKano Dutse ya riqe muqamin Ministan Mulkin En'e sai ya qara bunqasa horo da Sarakuna ke samu da quma yawon buxe ido.

Alal misali, a watan Oktoban shekarar 1958, wannan Ministа ya buxe wani Kwas na Sarakuna a *Lugard Hall*, Kaduna. Wanda ke tafiyar da wannan Kwas xin kuwa shi ne Mr. M.J. Campbell na Ma'aikatar Koyon Aikin Mulki ta Zariya, da mataimakinsa M. Yusufu Kazaure. A lokacin wannan Kwas ne manyan ma'aikatan gwamnati za su riqa yi wa Sarakuna lacca a fannoni daban-daban. Ta haka ne Sarakuna da shugabanni za su fahimci manufofin gwamnati da kuma yadda za su bada ta su gudunmawar wajen cimma manufa.

Sarakunan da suka halarci wannan Kwas kuwa su ne: M. Mbale, Sarkin - Vachama daga lardin Adamawa. M. Umaru Sarkin Katagum, da M. Malika Sarkin Dass daga lardin Bauci. M. Ahmadu Sarkin Kafi, da M. Muhammadu Sa'idu Sangarin Awe, da M. Atoshi Agbunamu Aka Uka na Wukari, da M. Sambo Gara na Donga daga lardin Binuwai. Alhaji Muhammadu Sani, Sarkin Borgu daga lardin Ilori. Alhaji Abdu Aguye Ohimegi Igu na Koton Qarfe, da M. Muhammadu Bawa Allah Aganshu na Kakanda, da M. Muhammadu Sani Olomori na Igbirra daga lardin Kaba. M. Muhammadu Bello Sarkin Paiko, da M. Alasan Sarkin Gunna, da M. Muhammadu Bello Sarkin Agaye daga lardin Neja. M. Panzhi Taroh Sarkin Yergam, da M. Abdullahi MaiKano, Sarkin Wase, da Mark Hirse, Sarkin Sura Pyem, da M. Musa Sarkin Mada, da M. Muammadu Kwori Sarkin Wamba daga Qasar Kuza. M. Jibrin Sarkin Birnin Gwari daga lardin Zariya.[1]

A lokacin wannan Kwas, Sarakuna sun saurari laccoci daga manyan ma'aikatan gwamnati a Jiha. An kuma yi amfani da wannan dama wajen sanya Sarakuna zuwa yawon buxe ido. A dalilin haka ne suka riqa ziyarce-ziyarce na waye kai. Sarakuna sun ziyarci maxaba ar gwamnati, Gidan Rediyo inda suka yi

[1] GTK, 10/10/1958 shafi na 9

jawabi a shirin nan na `Baqin Kaduna'. Har ila yau sun ziyarci wurin Binciken Kaji. An kuma nuna masu siniman mulkin En'e.[1] Duk waxannan matakai sun taimaka wajen qarawa Sarakuna ilimi da wayewar kai waxanda babu shakka sun taimaka masu gaya wajen gogewa akan harkar mulki.

Daga qarshe sai Mr. A.T. Weatherhead Muqax*da shi*n gwamnan Jihar Arewa da Ministan Mulkin En'e M. Abdullahi MaiKano Dutse suka yi masu liyafa.[2] Wato sun qare Kwas xinsu ke nan. A wannan lokaci sai Ministan ya yi jawabin rufe wannan Kwas. A cikin jawabinsa ya ce musu, a cikin mako biyu da kuka yi kuna wannan Kwas, kun sami sami damar shaquwa da juna da kuma jin tausayin juna kan wahalhalun da ku ke sha kan waxansu abubuwa.

Har ila yau kuma ya ce musu, "a Kwas xin nan kun sami damar jin labarin cin nasarar da waxansu Sarakuna suka yi wajen Aikin Raya Qasa da Mulkin En'e, wanda qila ku kwaikwaye su." Ministan ya ce yana son su yi dogon tunani qwarai kan abubuwan da aka gwada musu, sa'an nan su duba su ga yadda zai amfani mutanensu. Daga qarshen jawabinsa Ministan ya faxi muhimmancin qarfafa En'e-En'e, wanda ta hanyar mulki mai kyau ne za su sami amincewar jama'a. Ya kuma faxi buqatuwa En'e ta yi tafiya tare da zamani, ta kuma nuna biyayya ga gwamnatin Jiha. Ya ce, "To, kada a yi kuskure, yanzu ne ma muka dulmuya cikin aikinmu. Mulkin Kai, abu ne mai ban al'ajabi da za mu maida himma kansa, amma idan mulkin kan ya zo ran 15 ga Maris baxi, ko kusa wahalhalun da mu ke sha baza su ragu ba. Tilas ne mu zage sosai don mu samawa qasarmu arziqi."[3]

Kwaleji ta Ahmadu Bello

Firimiyan Jihar Arewa ne ya aza harsashin ginin kwaleji ta Ahmadu Bello wadda za ta zama cibiya kuma xaya daga cikin kwaleji-kwaleji na Jami'ar Jihar Arewa. Kwaleji xin an raxa mata sunan Firimiya ne saboda yabawa da iya shugabancinsa da kuma babban aiki maras iyaka da ya yiwa Jihar nan. Bikin aza harsashin nan mai qayatarwa an yi a bayan ganuwar Kano ne kusa da qofar duka wuya. A wajen aza harsashin, Firimiyan Jihar Arewa ya ce:

"Da sunan Allah na aza harsashin, ginin wannan jami'a wadda ni ke roqo ta kawo amfani mai xorewa abadan wajen ilimi mai zurfi ga mutanen Jihar nan."[4]

Wannan muhimmiyar addu'a sai ta zama ruhin wannan jami'a don ta shahara a duniya. Tun farko kafin ya aza harsashin a cikin jawabinsa, Firimiya ya bayyana

---

1 *Ibid.*

2 *Ibid.*,

3 *GTK* , 31/10/1958 shafi na 8

4 *Ibid.*, 21/10/1960, shafi na 1

godiyarsa ga Ministan Ilimi kan abubuwa masu kyau da ya faxi game da shi . Ya ce komai ya yi a qasar nan, ba ya yi shi kaxai ba ne, a'a, ya yi ne da goyon bayan Ministoci, da Sarakuna, da 'yan Majalisar Wakilai da kuma sauran mutanen Arewa.

Wannan ranar alfahari ce gare shi Firimiya ya ce, "don kuwa mutane kaxan ne, idan ma akwai, aka darjanta su a lokacin da suke cikin zamaninsu na duniya kamar yadda aka yi masa aka raxa wa wannan muhimmiyar makaranta sunan sa." Abin da ya qara qwarzanta wannan sha'ani inji Firimiya, shi ne yadda haxaxxen taron 'yan Majalisar Dokoki suka yarda a sanya wa kwalej xin sunan sa ba tare da jayayya ba. Wannan batu na amincewa ya sanya shi alfahari. Sardauna ya cewannan ke sanya shi ya zama mai tunani don kuwa ya gane cewa haqqinsa kamar yadda zai zama cikin jin daxinsa ya ba da qarfinsa ga wannan kwalej a shekaru na gaba, Ya ce: "Da taimakon Allah Ubangiji zan ci nasara." Ya kuma ci nasara sosai a wannan shirin na sa.

Sir Ahmadu Bello ya ce, yana jin daxi musamman da aka girmama shi ta wannan hanya, don kuwa yana jin cewa girmamawa ce ga dukkan iyalan Shehu Xan Fodiyo da kuma shi kansa Firimiya. A wannan lokaci kuma ya ce"Majalisar Jami'a ta Ibadan sun yi kirki da suka sanya sunan kakan ka kansa daga cikin gine-ginensu, "Zauren Bello." Sardauna na jin cewa yana riqe da xaukakan nan na danginsa da ya xauki sha'awar ci gaban ilimi.

A game da shi rahoton Hukumar Ilimi mai zurfi na Ashby kuwa sai Firimiya ya ce ba dai-dai ba ne gare shi ya faxi wani abu game da shawarwarin da Hukumar ta bayar, amma wajibi ne mutum ya duba abin da ke cikin rahoton don "zai kawo mana gagaruman matsalolin ilimi da ya fuskance mu duka da wannan jiha musamman." AmmaFirimiya ya yi maraba da abubuwan da Hukumar ta hango.

Firimiya ya ce, "a cikin shekaru goma da suka wuce, mutanen Jihar nan sun yi qasaitacciyar himmar buxe ilimin Turawa ta kowace hanya, makarantun sakandare da na Firamare sun ruvanya har sau uku, sa'an nan an fara yin azuzuwa shida."[1]

Daga qarshe Firimiya ya jawo hankalin mutanen jiha cewa im ba tare da qwazo da dauriya ba na gwamnatinsa, da En'e-En'e da Mishan da jama'a daban-daban ba, da bai yiwuwa a yi makarantun sakandare da na Firamare da'a ke buqata ba. Haka kuma in ba tare da nuna hali mai kyau a gidaje, babban haxa kai na iyaye, da ba da kan kowa da kowa, to, da Gwamanati ba ta yi komai ba. Firimiya yana so a xauki wannan biki ya zama hanya ce ta kira ga kowa ya gyara kura-kuran da ke cikin neman ilimi. Wannan rana ce ta tarihi.

---

[1] GTK 21/10/1960, shafi na 1

Yanzu ne bukukuwan 'yanci, Firimiya ya ce saboda haka dadai ne a yi shagalin wannan rana ta tarihi, amma kamar yadda yake cewa a wata harkar, 'yanci ga kawo haqqinsa na kansa, waxannan kuwa ba za a iya xaukarsu ta hanyar sauqi ba sai muddin muna da mutane maza da mata masu ilimi da za su xauki ayyukansu da ake buqata na raya Jiharmu.

Game da haxa wannan kwalej da Jami'ar Arewa, wannan makaranta za ta tanadi koyon ilimin Arabiyya da na Turawa, lokacin da take bunqasa. Kuma Musulmi da Kirista za su yi xalibta kafaxa da kafaxa wanda zai yi babban taimako na haxa kan wannan Jiha da Tarayya baki xaya.

Firimiya daga qarshe ya yabawa Mr.Whitting wanda ya kira,"wannan qasaitaccen mutum," ya koya wa Firimiya, da Firayim Minista, da Sarkin Gwandu, da Ministan ilimi da sauran mutane da dama da ke cikin aikin gwamnati. Wannan mashahurin malamin makaranta, ya daxe a Arewa yana aikin koyarwa, ya kuma taimaka ga ya wajen bunqasa ilimi a wannan jiha. Sardauna ya kuma yaba wa marigayi Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayero wanda xan'uwansa ne da ya yi qasaitaccen taimako na qarfinsa da kuxi ga ci gaban makarantar ilimin Arabiyya wadda yanzu za ta zama kwalej ta Ahmadu Bello. Ya ce ya yi murna qwarai da Sarkin Kano na yanzu, Alhaji Sir Muhammadu Sunusi yake bin sawu iri xaya wajen ilimi. Shi ma ya tafa albarkacin bakinsa, a wannan muhimmiyar rana.

A cikin jawabinsa Sarkin Kano ya ce:

> *Wannan abin da shi da duka mutanen Kano za su yi alfahari ne. Da farko za su yi farin ciki don Jami'ar Jihar Arewa da ake niyar yi am fara ta daga Kano. Sa'an nan na biyu saboda kwalej xin an raxa mata suna kwalej ta Ahmadu Bello don tunawa da Sir Ahmadu Bello Firimiyammu da mu ke qauna, yaci gaba da cewa ba tantama ya yi ayyuka masu amfani ga wannan qasa, saboda haka ya cancanci yabo da karramawa.*
>
> *Makarantar ilimin Arabiyya, shekaru da dama tana nan, yanzu an xaga ta zuwa kwalej ta jami'a ta Jihar Arewa da ake niyyar yi. Wannan qoqarin Shehunan Sudan ne da Malaman qasar nan da suka koyar a makarantar musamman Malam Bashir, Alnur da Muhammad waxanda da su ne aka fara buxe makarantar. Kuma ina godewa Mr. Whitting da Hiskett kan aikin da su kayi a makarantar. Na yi kuma yi farin cikin ganin su duka a wannan biki.*
>
> *Shugaban Makarantar na qarshe shi ne Shehu Awad wanda ba shakka ya yi aiki mai amfani, kuma abin farin ciki ne da yanzu ya*

zama Babban Alqalin Jihar Arewa, wanda kuma ya gaje shi M. Aliyu Abubakar tsohon xan makaranta ne. [1]

Daga qarshe Sarkin Kano ya taya Firimiya murna da ya ba da sunansa ga kwalej xin don tunawa da shi kansa. Wannan biki na tarihi ne wanda har abada ba za a manta da shi ba a wannan qasa. Bayan Sarkin Kano ya qare,sai Alhaji Isa Kaita, Ministan ilimi ya miqe ya kira wannan babbar rana ce ga ofishin Ministan Ilimi na Jihar Arewa, Ya ce zai ci gaba da cewa ma wannan babbar rana ce ga dukkan waxanda su ke aikin sha'anin ilimi ba a Arewa kaxai ba har da Nijeriya gaba xaya.

Ministan ya ce, "an taru a nan da farko don a gode wa Firimiyanmu wanda shi ne Uban ilimi, haka kuma a roqe shi ya aza harsashin gina sabuwar kwaleji wadda za a santa da sunansa. Na biyu, kuma shi ne a nuna wa duniya qoqarinmu na inganta ilimin Arabiyya da na Turawa a Jihar Arewa."

Ministan ilimi ya qara da cewa ilimi ne tushen manufar koya wa samari daga dukkan lardunan Arewa don su xauki matsayin su wajen ayyukan gwamnati. Alhaji Isa Kaita ya kuma faxi irin shawarwarin da Sir Ahmadu Bello ke ba shi lokacin da yake tafiyar da aikinsa na hanzari mai rikitarwa. Ya faxi cewa Sir Ahmadu Bello ya yi shekaru da dama yana koyarwa, kuma barin aikin koyarwa da ya yi ya dace. Amma yana fata ba dukkan Malamai ba za su kwaikwaye shi ba.

Makarantar ilimin Arabiyya, Ministan ya ce makaranta ce da babu kamarta a Afirka, don kuwa tana koyar da tarihin musulunci, da shari'ar musulunci, da Larabci, da Tauhidi, da koyon Malanta da Turanci. Ya bayyana rubutun da aka xebo cikin Alqur'ani da aka yi kan tubalin harsashin ginin da, ya ce ma'anarsa shi ne "Komai ilimin mutum akwai wanda ya fi shi." Saboda haka yana fata bayan qarnonin da za su wuce, wanda za su ci nasarar makarantar za su kula da wannan rubutu kuma su tuna cewa ilimi ba ya da qarshe.

A lokacin da Firimiya ya aza harsashin ginin sai aka yi karatun Alqur'ani. Alhaji Sir Abubakar na Uku ya rufe taron da addu'ar Allah Ya albarkaci wannan makaranta. Allah Ya amsa wannan addu'a da Manyan Malamai da Sarakuna da shugabanni suka yi. Manyan mutane sun halarci wannan muhimmin biki. Cikin waxanda suka halarci bikin har da Gwamna- Janar na Nijeriya, da gwamnan Jihar Arewa, da, da Firayim Minista, da Sarakunan Gwandu, Katsina, Zazzau, Ilori, Lafiya, Gumel, Kazaure, Atta na Igala, Etsu Nupe, da Ministocin Jiha da sauransu.[2]

Firimiya ya aza harsashin wannan kwaleji cikin nasara da sa'a, Allah Ya kuma karvi addu'o'insa da na jama'a da manyan baqi suka yi. Wannan kwaleji ta zo dai-

---

[1] GTK 21/10/1960, shafi na 1

[2] GTK 21/10/1960, shafi na 6.

dai lokacin da ake shawarwarin kafa jami'a a Arewa. Ana so a haxa kwalejin Arewa don su zama jami'a. A wannan shiri sai kwaleji ta Ahmadu Bello da ke Kano ta zama ruhin wannan jami'a saboda ita ke xauke da addu'arsa da kuma sunansa, a qoqarinsa na bin sawun kakannin-kakanninsa kamar Muhammadu Bello wajen yaxa ilimi da Addinin musulunci.

A shekarar ta 1962 sai aka mayar da Kwalejin Ahmadu Bello qarqashin Jami'ar Ahmadu Bello Zariya, sai kuma aka juya mata suna zuwa Kwalejin Abdullahi Bayero. A shekarar 1975 ta sami wani vangare na matsayin jami'a, amma sai a shekarar 1977 wannan kwaleji ta zama cikakkiyar jami'a da sunan Jami'ar Bayero, Kano.

Shirin Kafa Jami'ar Jihar Arewa

A shekarar 1959 Alhaji isa Kaita, Wazirin Katsina Ministan Ilimi na Jihar Arewa, da Alhaji Aliyu Makaman Bida, da Mr. Michael Audu Buba, Wazirin Shendam, da Alhaji Ahman, Galadiman Pategi, da Alhaji Umaru Vavura, Sarkin Fulanin Ja'idawa, da Alhaji Ahmadu Fatika Sarkin Fadan Zazzau, da Alhaji Aliyu, Turakin Zazzau da sauran manyan mutane ne suka haxu suka tattauna yadda zasu karrama Alhaji Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato Jikan-Jikan Mujaddadi. A wannan zama ne suka zartar da umurnin cewar a kafa wata babbar Makaranta wadda za a sanyawa sunansa.

A kuma wannan shekara ce gwamnatin Tarayya ta kafa Hukumar Kula da Ilimi Babba a Nijeriya wato, the Ashby Commission on Higher Education in Nigeria. Ita wannan Hukuma sai ta buqaci Arewa da ta aiko mata mutum guda wanda zai wakilce ta. Ba a vata lokaci ba wajen aikawa da sunan Sanata Shettima Kashim, Wazirin Barno, wanda ya tava riqe muqamin Ministan Ilimi da Jin Daxin Jama'a na Tarayya. Ita kuma wannan Hukuma sai ta bada umarnin da, Hukumar Kula da Jami'o'i ta qasa wato National Universities Commission (NUC) ta shiga tattaunawa da gwamnatin Tarayya da Jihar Arewa da niyyar kafa jami'a a Arewa a Zariya. Don a taimaka wajen kafa wannan jami'a, gwamnatin Tarayya ta bada reshen Kwalejin Kimiyya da Fasaha da ke Zariya ga gwamnatin Jihar Arewa.

Ita kuma Jihar Arewa tare da taimakon gwamnatin Tarayya sai ta nemi shawarar Sakataren hulda na qas ashen Commonweath. A dalilin haka ne sai a shekarar 1961, Inter-University Council (IUC) ta London ta aiko da wata tawaga qarqashin jagorancin Sir Alexander Carr-Sanders, wani tsohon shugaban London School of Economics don ya ziyarci jihar Arewa. Ita wannan qungiya sai a watan Afrilu na shekarar 1961 ta bada umarnin da a kafa jami'a a Arewa.

A watan Yuni 1961, a lokacin haxaxxan zama na Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai, sai Ministan Ilimi Alhaji Isa Kaita ya gabatar da Batu na kafa jami'a a Jihar Arewa a kuma sanya mata sunan Firimiya, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato. Hadaxxiyar Majalisa ta karvi wannan batu gaba xaya ba tare da wata jayayyaba. Haka kuma bayan gwamnatin Tarayya ta bada Kwalejin Kimiyya da Fasaha sai ta qarawa Jihar Arewa da Makaranta Koyon Aikin Mulki duk su haxe da wannan sabuwar jami'a

A watan Nuwamba 1961 aka kafa hukumar kula da wannan jami'a wato University Council. Mai girma Alhaji Shettima Kashim shi aka naxa shugaban wannan Hukuma na farko. Amma da ya zama gwamnan Arewa xan qasa na farko, sai shugabancin University Council ya koma ga hannun Sarkin Bedde, Mai Umar Ibn Sulaiman. A kuma farkon watan Yuli na shekarar 1961, aka naxa Dr. Norman S. Alexander a matsayin Principal daga baya ya zama Mataimakin Shugaban Jami'a wato Vice-Chancellor na farko.

A ranar 4 ga Oktoba 1962 aka naxawa wannan Babbar Makaranta suna Jami'ar Ahmadu Bello wato Ahmadu Bello University. A dalilin haka ne sai aka kashe tsuntsaye biyu da dutse guda. An karrama Sardauna an kuma qara faxaxa ilimi a Arewa, ta manufofin wannan mashahuriyar jami'a.

A lokacin da wannan jami'a ta taso tana da: Kwalejin Abdullahi Bayaro, inda ake koyarda Ilimin Addinin Musulunci da Larabci; Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya; Cibiyar Binciken Aikin Gona ta Samaru Zariya; Cibiyar Binciken Cututtukan Dabbobi a Vom. Wannan jami'a sai ta taso da kwarjini da buwaya irin na Shugabanta Sir Ahmadu Bello. A ran 27 ga Agusta 1967, gwamnatin Mulkin Soja ta Tarayya ta karve Ahmadu Bello University, ta zama jami'ar Tarayya ba ta Jihar Arewa ba.[1]

gwamnatin Tarayya ta Kafa Hukumar Kula da ilimi a qarqashin shugabancin Sir Eric Ashby. Wannan Hukumar ta qunshi; Professor Kenneth Onwuka Dike, Sanata Shettima Kashim; Dr. Sanya Onabamiro; Professor R.G Gustavon; Professor H.W. Hannah, Dean F. Feppel; Sir J.F. Lockwood and M.G.E. Watts. Haka kuma tana samun taimakon Professor F. Harbison da Mr. M.W. Pitchard, Sauran masana da ke taimakawa wannan Hukuma sun haxa da Mr. V.L Griffiths; Professor J.N.D Anderson. Duk waxannan masana sun gabatar da qasidu daban daban akan yadda za a tafiyard da harkokin ilmi da zai dace da wannan qasa.

Kwamitin Binciken ilimi mai zurfi wanda gwamnatin Tarayya ta tanada a qarqashin Sir Eric Ashby ta qare aikinta har ta miqa rahotonta. Cikin muhimman

[1] .U. Akaa Niro, Isa Kaita, Wazirin Katsina, shafi na . 86, 88 and 90

shawarwarin da ta bayar har da maganar kafa Jami'ar Jihar Arewa wadda za ta kasance a Zariya. Wato Kwalejin Ilimin Kimiyya da Fasaha, reshen Zariya a ke so ta zama Jami'ar, sa'an nan kuma a sami haxa kai da kwalej ta Ahmadu Bello a Kano, da makarantar Binciken Aikin Gona ta Samaru, da makarantar Binciken Ciwon Dabbobi a Vom, da kuma makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya.[1] Waxannan makarantun ne aka xungule su suka zama mashahuriyar Jami'ar Ahmadu Bello.

Game da ilimin Firamare, kwamitin Ashby ya ga wajibi ne a riqa samun yara da dama da za su shiga makarantun Sakandare, ya ce ya kamata a Jihar Arewa a xauki hanyar farko ta qara yawan, masu ilimin Firamare a shekarar 1970.

Wajen ilimin Sakandare kuwa, kwamitin ya ce don a sami masu fita da yawa, dole a hanzarta qara yawan xaukar yara daga dubu goma sha-biyu (12,000) a shekarar 1958, zuwa fiye da dubu talatin (30,000). In ana son yin haka, Kwamitin ya bada shawarwari a sami makarantun Sakandare xari shida (600). Ta kuma qiyasta cewa daga cikin yara dubu ashirin da tara (29,000) da za su gama Kwas na "School Certificate" kowace shekara idan dai aka bi hanyar qara yawan masu shiga Sakandare, yara dubu ashirin da xaya (21,000) za su sami aiki, sa'an nan kamar dubu takwas (8,000) za su je qaro ilimi. Har ila yau kuma daga cikin dubu takwas (8,000) xin kamar dubu uku da xari biyar (3,500) za su yi Kwas na Babban Satifiket ko *General Certificate of Education*.[2]

Kan ilimin sana'a, kuwa kwamitin ya ba da shawara da a riqa samun masu fita sakandare suna shiga koyon ilimin sana'a, yadda har za a sami yara dubu biyu da xari biyar (2,500) kowace shekara da ke shiga Kwas na ilimin sana'a.

Wajen inganta jami'a a Nijeriya, ya ba da shawara daga shekarar 1970 a riqa samun yawan xalibai dubu bakwai da xari biyar (7,500) masu shiga Jami'a. Dukkan jami'o'i na Nijeriya kuma su zama na qasa ne gaba xaya ba tare da nuna bambancin qabila ko Jihar da mutum ya fito ba. Wannan Hukumar ta kuma bada shawara da jami'o'in su kasance suna da 'yancinsu, kuma kowace taba da digiri xinta. Wato kowace jami'a ta ci gashin kanta. A wajen yawan jami'o'i kuwa, kwamitin Ashby ya ba da shawara da a sami jami'o'i huxu a Nijeriya da za a riqa samun xalibai dubu biyu (2,000) a shekara. Wani babban jigo a cikin wannan kwamiti wanda ya taka rawar gani, kuma mashahurin xan Arewa ne, wanda ba za a manta da shi ba kuwa shi ne Wazirin Barno Shettima Kashim.[3]

Majalisar Sarakuna a zaman da ta yi na musamman ta zartar da dokar kafa Jami'ar Ahmadu Bello ta shekarar 1962. Ita wannan doka, 'yan Majalisar Wakilai

---

1 GTK 14/10/1960

2 GTK 14/10/1960

3 *Ibid*.

ne suka fara zartar da ita. A lokacin zaman da Wakilan suka yi, Mai girma, Firimiyan Jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello ne ya gabatar da wannan doka a gabansu. A wannan lokaci ne Sardauna ya cewa Wakilai za a kafa jami'a saboda 'ya'yan wannan jiha, da 'ya'yan da ke wajen jiha. Shirin kafa wannan jami'a, ya samo asali ne shekaru tara da suka wuce. A shekarar 1952, akwai makarantun sakandare uku kacal a Nijeriya ta Arewa, amma yanzu akwai fiye da guda hamsin, ya ce Ministan Ilimi ma, na ci gaba da faxaxa harkokin ilimi a Arewa.

Firimiya sai ya miqa godiyarsa ga Ministan ilimi na Jihar Arewa na farko wanda ya zama Ministan Kuxi wato Alhaji Aliyu Makaman Bida da gwamnan Arewa Sir Kashim Ibrahim, waxanda suka taimaka gaya wajen ganin wannan shiri ya cimma nasara. Ya kuma yi nuni da Kwalejin Fasaha, inda ya ce Sir Kashim yana Xaya daga cikin ginshiqin da suka kafata suka kuma tallafa mata. Sardauna ya yaba wa qoqarin Dr. N.S Alexander da Ministan Ilimi, Alhaji Isa Kaita, Wazirin Katsina.

Sarakuna da yawa sun yi tsokaci akan dokar da Majalisar ta zartar, sun kuma yi addu'ar samun nasara ga wannan jiha da ta kawo kafa wannan Jami'a, inda suka yi godiya ta musamman ga namijin qoqarin da Firimiya ke yi. Sa'an nan suka yi na'am da sunan "Ahmadu Bello" a matsayin sunan Jami'ar.

A lokacin da Sarakuna ke faxin albarkacin bakinsu sai Sarkin Paiko, Alhaji Muhammadu Bello ya cewannan dokar ci gaba ce kuma wata nasara ce babba ga Firimiya da Ministocinsa. Shi kuwa Sarkin Argungu, Alhaji Muhammdu Mera, kira ya yi ga jama'ar wannan jiha da su tallafi wannan jami'a. Sarkin kuma yana sa burin ganin gwamnatin jiha zata qarfafawa matasa masu hazaqa qwarin gwiwa, musamman waxanda ke aikin gwamnati da En'e don su samu damar zuwa jami'a. Ya cewannan ya zama wajibi saboda akwai ma'aikata masu yawa da iyali, waxanda ya kamata a mara wa baya don su qaro ilimi ta hanyar ba su tallafin kuxin alawus wanda zai taimake su kula da iyalansu.

Sarkin Lafiyagi, Malam Umaru Olu-Odde, ya yabi gwamnati ne musamman Firimiya inda ya ce: "Saboda samar da jami'a ga makekiyar jiha kamar wannan." Haka shi ma Sarkin Misau, Malam Ahmadu ya yi magana ne akan goyon bayan wannan doka, kuma ya umurci cewa ayi qasaitaccen biki wajen buxe wannan jami'a, a kuma maida wannan rana, ranar hutu a duk faxin Arewa. Sauran Sarakunan da suka yi maganar yabo da fatan nasara ga Firimiya da wannan jami'a sun haxa da:

Sarkin Nasarawa Eggon, Alhaji Abdullahi Idde, da Sarkin Bunu, Mr. J. Adebayo Kusemoro, da Sarkin Idoma Mr. Ajene Ukpabi, wanda ya ce,"haqqi ne akan kowane xan Jihar nan ya ga wannan jami'a ta cimma muraxinta ta hanyar qarfafawa matasa zuwa makaranta."

Sardauna ya saurari kowane Sarki da ke tofa albarkacin bakinsa, sai ya basu amsar bisa ga abubuwan da Sarakunan suka faxi. Da farko dai sai ya yi godiya ga

Sarakuna da Shugabannin Arewa, a matsayin gwamnati, ya kuma gode masu matuqar gaske da goyon bayan da suke ba shi. Ya ce duk nasarorin da gwamnanti ta samu, sun yiwu ne ta hanyar haxin kan da ya samu daga abokan aikinsa, ba ta qwazonsa ba ya ce ai, "Bishiya Xaya Ba Ta Daji." A kan maganar Sarkin Misau da ya ba da shawarwari buxe jami'a da qasaitaccen biki, Sir Ahmadu Bello, ya ce, yin hakan ya dace kuma za a gayyato baqi daga qetare a lokacin wannan biki.

Daga nan sai ya gabatar da doka ga Majalisa ta tsaida shawarwari cewa, Majalisa ta amince da Kwalejin Nijeriya ta Al'adu, Kimiyya, da Fasaha, wato *Nigerian College of Science and Technology*, a mayar da ita bisa doka a shekarar 1962 da ta kuma fara aiki. Sir Ahmadu Bello ya tsai da shawara a kan haka ne zai baiwa gwamnati damar xaukar wannan Kwalejin. Ya qara da cewa an yi irin haka a sauran jihohin Tarayya. Haka kuma ya qara da bayyana cewa gwamnati za ta xauke wannan Kwalejin a ran 4 ga Oktoba na wannan shekara (1962). Bayan haka ne sai Majalisar ta tashi daga wannan zama.

gwamnatin Firimiya, gwamnati ce ta 'yan Siyasa da Sarakuna. A irin wannan samfurin mulki na Sarakuna a Siyasa 'yan siyasa na nuna halin Sarakuna. Haka kuma suma Sarakunan a wasu lokuta suna nuna halin 'yan siyasa. Saboda haxin kan waxannan Majalisu ta aiki da kyakkyawar manufa wadda ita ce ta kawo ci gaban Arewa da jama'arta ta kowace fuska.

Kafa Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariyana xaya daga abubuwan da Sardauna ya yiwa qasar nan na alheri da ba za a mance ba. An kafa wannan mashahuriyar jami'a a shekarar 1961 bayan an fara da kafa kwamitin nazarin batun ilimi mai zurfi na qasa a shekarar 1960. Ita wannan kwamiti ana kiranta *Ashby Commission*. Ita ce qungiyar da ta bayar da shawarwari kafa Jami'ar kuma tsohon gwamnan Jihar Arewa na da, Sir Kashim Ibrahim ya shugabanta, kamar yadda aka ba da labari.

Buxe Jami'ar Ahmadu Bello

An buxe Jami'ar Ahmadu Bello a ranar Alhamis 11 ga watan Oktoban shekarar 1962. Bikin buxe Jami'ar an yi shi ne a harabar Jami'ar da ke Zariya, wanda kuma ya buxe ta shi ne Firimiyan Jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello. Kafin ya gabatar da Mataimakin Shugaban Jami'ar Dr. N.S. Alexander (ya zama Sir), sai da Sarkin Bedde wanda shi ne Shugaban Majalisar Jami'ar, wato *Chairman of the University Council* ya xan yi taqaitaccen bayani, a inda ya nuna fatan wannan jami'a ba za ta zama mai daraja ta biyu ba, sai dai mai daraja ta xaya. Saboda, haka ne ya ce sai fa gwani ya dace da Arewa *Only the best is good enough for the north*.[1]

[1] NC, No. 1078. Asabar 13th October, 1962.

Sarkin ya ce abu ne da kowa ya sani a 'yan shekarun nan na Arewa ta yi abubuwan tarihi a fannoni masu yawa, musamman a fannin ilimi. Ya kuma yi godiya ga Sir Ahmadu Bello da Sir Kashim Ibrahim, tsohon Shugaban Majalisar Jami'ar. Daga nan sai ya gabatar da Mataimakin Shugaban Jami'ar Dr. Alexander.

A jawabinsa, Dr. Alexander, ya ba da xan yanki daga cikin tarihin wannan jami'a. Ya ce ta samo tushe ne daga Kwamitin Ashby na shekarar 1960, wanda ya haifar da doka da ta kafa Majalisar Jami'a ta wucin-gadi a shekarar 1961. Shugaban ya ce yana fatan wannan jami'a zata zama mafi daraja, ya kuma qara da cewa:

> *Tun kafin mu buxe qofofinmu, na yi imani da mun yi dai-dai da kowace jami'a wajen nagarta, in ma ba wajen yawa ba da kowace jami'a a Afirka.*
>
> *Jami'ar za ta zama cikin sahun jami'o'in duniya wajen halayya, ko da yake Jami'ar 'yan Arewa ce, nan gaba akasin xaliban da za a xauko su ne daga Arewa. Amma za mu gaza a muradinmu idan muka rufe qofarmu ga sauran jihohi.*
>
> *Haka kuma Malaman wannan jami'a za su dace da irin na kowace jami'a a duniya. A halin yanzu muna da malamai 'yan Nijeriya, da 'yan Ghana, da 'yan Afirka ta Kudu, da 'yan Pakistan, da Indiyawa, da 'yan Sudan, da 'yan New Zealand, akwai kuma 'yan Holland da Poland.*[1]

Dr. Alexander na gama jawabinsa, sai Firimiya ya buxe Jami'ar. Ya kuma ba da kyautar littattafai ga xalibai, ciki harda Alqur'ani mai Tsarki, da kuma litattafan kakannin kakanninsa, wato Shehu Usman Xanfodiyo, da Shehu Abdullahi Xanfodiyo, da kuma littattafan Rayuwata, wato *My Life* (Rayuwata).[2] Littattafan da ya rubuta akan rayuwar Sir Ahmadu Bello.

Ba da vata wani lokaci ba sai Jami'ar ta shiga gudanar da aiki gadan-gadan a cikin watan Nuwamba na 1961 zuwa 4 ga watan Oktoba shekarar 1962 Jami'ar ta zauna daram da gindinta. An kuma fara koyar da xalibai a ranar 10 ga watan Oktoba ta shekarar 1963. An fara da yawan xalibai guda xari huxu da ashirin da biyar (425). A kullum sai qara bunqasa take yi. Ta na kuma xaukar xalibai daga kowace Qaramar Hukuma a duk faxin tarayyar Nijeriya, wannan abun ne da ya zama gagara koyo ga sauran jami'o'i a Nijeriya.

Jami'ar ta fara aiki da "Faculties" guda huxu, da "Departments" goma sha-biyar, da "Institutes biyu", da "Centre" xaya. Ta kuma fara da malamai da ma'aikata da suka yi yawan xari da arba'in da biyu. Sir Ahmadu Bello shugaban

---

1 NC, No. 1078. Asabar 13th October, 1962.

2 *Ibid*.

Jami'ar Kuma Firimiyan Arewa ya bayyana maqasudin kafa wannan jami'a da kalami kamar haka:

Maqasudin kafa wannan jami'a shi ne domin ta ba da ilimi ga maza da mata na kowace jinsi ba tare da nuna bambancin launin fata, addini ko aqidar siyasa ba. Duk waxxan nan sharuxxai na cikin dokokin jami'a. Sai fa da 'yancin bincike ne jami'a za ta iya yin tunani da qirqiro da sabuwar hanya ko ilimi. Sai fa kuma ta jajirce akan 'yancin yin bincike ne jami'a za ta shahara. Idan aka xauko malamai da xalibai daga sassan duniya aka kuma haxa su waje guda a qarqashin inuwar ba da ilimi sai a sami jami'a da za ta cimma muradinta.

Wannan Jami'a ce da aka kafa da Basmallah don haka sai ta tashi da qasaita da shahara a kullum sai hamdala ake yi da kafa ta. Kamar yadda aka yi bayani ne an haxe manyan makarantu biyar ne wajen kafa ta wato Kwalejin Ahmadu Bello ta Kano, da kwalejin Ilimin Kimiyya da Fasaha ta Zariya, da Makarantar Binciken Aikin Gona ta Samaru, da Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya da Makarantar Binciken Ciwon Dabbobi ta Vom. Kafin ta cika shekara hamsin da kafuwa har ta qasaita duniya ta santa. Saboda ta na da kyakkyawar niyya. Burin wannan jami'a shi ne a faxaxa fannonin ilimi, a kuma qirqiro sabbi ta koyarwa da bincike tare da yaxa ilimi mafi daraja. Sa'an nan a samar da haxin kai a tsakanin wannan qasa da qasashen qetare da kuma havakar da al'adu da xabi'un Afirka. Don ta zama abar misali da alfahari ga al'umma wajen yaye 'yan mata da samari zarata masu ilimi.

An qiyasta ta na da yawan xalibai dubu arba'in (40,000) a shekarar 2007 wato ta ruvanya yawan xaliban farko sau xari ke nan bayan shekaru hamsin da kafata. Xalibanta kuma suna zuwa daga sassa daban-daban na duniya. Ita ce jami'a mafi yawan xalibai a Nahiyar Afrika Kudu da Sahara. Ta kuma yaye dubban xalibai da suka yi suna a duniya a fannonin ilimi daban-daban.

Buxe Xakin Karatu da Makaranta

Firimiyan Jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato, ya gudanar da wani taqaitaccen bikin buxe sabon xakin karatu a ran 19 ga watan Afrilun shekarar 1963. Xakin karatun ya ci kuxi fam dubu talatin da biyar (£35,000). gwamnatin Arewa da babban ofishin Jakadanci na Birtaniya ne suka haxa gwiwa wajen gina shi, kuma shi ne xakin karatu na farko a Arewa.

Da yake jawabi, Firimiyan Jihar Arewa, ya ce an gina xakin karatun ne amatsayin wani vangare na qoqarin da gwamnatinsa ke yi na ba da babbar gudunmawa ga shirin ilimi a Qasar nan, tare da baiwa dukkan wanda yake burin karatu neman ilimi ya yi abota da xakin karatu domin kyautata darajar iliminsa.

Sardaunan Sakkwato, ya kuma ce a da jama'a na fuskantar matsaloli a kowane wajen samun bayanai a game da sauran qasashe musamman kayayyaki da suke yi don saidawa, da cinikayya, da qerawa a vangare daban-daban, sai dai abin farin

ciki shi ne a yanzu wannan sabon xakin karatu zai samar da wadatacciyar kafar samun bayanai a kan ci gaba da dama, kamar su fannin kayayyaki, da qwarewa daban-daban ta jama'a. Tunda farko sai da Sir Ahmadu Bello ya yi marhabin da xakin a matsayin wani babban qarin ci gaba ga muhimman abubuwan more rayuwa na Jihar Kaduna da kuma Arewa baki xaya.

A jawabin da ya yi tunda farko, Ministan yaxa labaru na Jihar Arewa, Alhaji Ibrahim Biu, ya taya ma'aikatar ayyuka da waxanda suka gina xakin karatun, wato kamfanin D. Alberto da Bogeilla, yin murna saboda kyawawan ayyukan da suka gudanar.

Daga nan sai Alhaji Ibrahim ya yi fatar xakin karatun zai zama mai muhimmanci ga ayyukan da sashen xakin karatu na ma'aikatarsa ke gudanarwa a halin yanzu haka, tare da qarin bayanin cewa ma'aikatarsa za ta gina xakin bada aron litattafai da shaqatawa da xakunan karatu a wannan waje da aka kammala wannan domin samar wa masu karatu da ke ko'ina cikin faxin Arewa litattafan da ke kan gaba domin karatu.

Ministan har ila yau ya godewa babban jakadan qasar Birtaniya wanda ta hannunsa ne, gwamnatin Birtaniya ta bada gudunmawar litattafai ga wannan xakin karatu. Ministan ya yi bayanin cewa a halin yanzu haka yana nazarin wani cikakken rahoto a game da bunqasa xakunan karatu a Arewa da wasu fitattun qwararru suka bayar tare da fatan rahoton zai zama mai muhimmancin gaske da alfanun gaske ga yankin.[1]

Waxanda suka halarci wannan gagarumin biki su ne wasu daga cikin Ministocin yanki, da Sakatarorin Majalisun Dokoki, da Shugaban Majalisa Alhaji Umaru Gwandu, da Sarkin Katsina Sir Usman Nagogo, da Atta na Igala, Mr Ali Obaje, da Manyan qusoshin gwamnati.

Buxe Makarantar Ma'aikatan Lafiya

Firimiya har ila yau a wajen wani taro mai armashi a Kaduna ya buxe wata makaranta ta horas da Ma'aikatan Lafiya da wajen qananan xalibai a kan kuxi fam dubu xari da hamsin (£150,000).

Da yake jawabi a wajen, Firimiyan ya ce, "Makarantar wacce aka soma buxe ta a watan Yuli na shekarar 1957, da xalibai talatin da shida (36) kawai, zuwa yanzu ta horas da xalibai xari biyu da arba'in da xaya (241) a fannin kiwon lafiya, sai malamai su wajen xari biyar (500) da aka horas a vangaren kuturta da ma'aikatan tallafi da suma aka koyar a makarantar." Sir Ahmadu Bello yaci gaba da cewa,"makarantar ta samu gagarumar nasara wanda za a iya gani a yadda xakunan shan magani ke qara yawa har a yankunan karkara a ko'ina cikin faxin Arewa."

[1] NC, No. 1129, 24/4/1963.

Daga nan sai ya yi nuni da cewa makarantar ta horas da qananan xalibai masu tallafawa ayyukan kiwon lafiya da ma'aikatan gwamnati da kiwon lafiya da ke aiki a vangaren lafiya. Bayan haka sai ya miqa gaisuwar ban girma ga Dr. G.K.M Khomo, shugaban makarantar tun da aka kafa ta a shekarar 1957. Sir Ahmadu Bello, ya kwatanta Dr. Khomo a matsayin mai gaskiya da aiki tuquru wanda a qarqashin jagorancinsa ne aka samu gagarumar ci gaba.

Da ya juya ga xaliban, Sardaunan ya hore su da su sanya tausayin talakawa gaba da komai a aikinsu saboda aikinsu ba qaramar martaba yake da ita ba, wanda idan suka tsaya suka dage suka yi aiki tsakaninsu da Allah, za su samu babbar lada a ran gobe qiyama. A jawabin da ya yi tun da farko Ministan Lafiya, Alhaji Ahmad Pategi, ya ce za a ci gaba da faxaxa ayyukan lafiya a yankin Arewa.

Firimiya, ya ba ilimi fifiko a ayyukan ci gaba da ya yiwa Jihar Arewa. Domin kuwa ilimi shi ne ginshiqin ci gaban kowace al'umma. A zamanin mulkin Sir Ahmadu Bello, zirga-zirga da sadarwa a tsakanin Arewaci da kudancin Kaduna nada wuyar gaske. Domin haka ne ya ga ya zama wajibi ya gina kadarkon mota a kan kogin Kaduna. Yin haka ya zama wajibi ga gwamnatinsa wadda ke da gagarumin shirin kafa Masaqar Kaduna a kudancin wannan kogi.

Kadarkon Mota

Shika-shikan ayyukan Sardauna guda biyu ne rak, su ne "Aiki da Ibada. Saboda haka ya duqufa wajen yaxawa da zurfafa ilimi. Domin ilimi shi ne ginshikin Aiki da Ibada. A wajen fuskar aiki, Sardauna ya yi gagarumin shirin gina masana'antu waxanda za su samawa dubban 'yan Arewa da 'yan Nijeriya aikin yi. A wannan shirin bunqasa masana'antu a kudancin Kaduna, sai Sardauna ya gina babban kadarko da zai haxa Arewaci da kudancin wannan gari.

Tun da aka gina gadar jirgin kogin Kaduna a cikin shekarar 1911, Turawan Ingilishi ba su yi tunanin yin gadar motar ba ko kaxan. Tun cikin shekarar 1921 aka yi ta rubuta takardu a game da a yi gadar mota, amma ba a yi komai ba. Har ya zuwa lokacin da aka gina gadar motar kogin Kaduna, wadda ita ce ta haxa sashen Arewa da na Kudu na wannan hedkwatar ta mu. Da can duk motoci da da 'yan amalanke da masu tafiya da qafa duk takan gadar jirgi suke qetarewa. Bisa gaskiya kuwa waccan gadar ta Reliwai ce, don haka a koda yaushe an fi bai wa jirage damar su wuce kafin kowa ya wuce. Ba yadda kuwa za a yi idan dai aka yi wa jirgi qararrawa tun kamar saura rabin sa'a ya iso, sai a dakatar da masu motoci da babura da kuma masu basukurori da masu tafiya a qasa har sai jirgin ya wuce.

Kafin a gina gadar mota akan wannan kogi, mutanen Kaduna sun sha wahalar zirga zirga tsakanin Maqera da Sabon Garin Doka. Saboda an sami shekaru arba'in da shida ana amfani da hanyar jirgi, abin da yake da haxari sosai, musamman idan aka yi la'akari da yiwuwar haxarin mota da jirgi akan wannan gada. Ko da yake an xauki matakan hana yiwuwar irin wannan haxari mai muni.

A wurare daban-daban akan hanyar jirgi inda ta haxu da ta hanyar mota an sanya alamomi da za su nuna jirgi na tafe ko kuma ya kusan zuwa. Saboda haka a duk inda hanyar mota ta qetare hanyar jirgi, wajen da ake kira *Railway Crossing*, akwai ma'aikatan Reluwe da ke hana qetare hanyar idan aka samu saqon tangaroho da ke cewa jirgi na tafe. Saboda haka sai a dakatar da zirga-zirgar mutane da abubuwan hawa har sai bayan jirgin ya wuce sa'an nan a buxewa jama'a hanya.

A duk inda hanyar jirgi ta haxu da hanyar mota a kan kunna jar fitila wadda take nuna cewa wajen na da haxari, saboda haka a lura an zo "Railway Crossing." Jama'a kuma sun san waxannan wurare saboda a duk lokacin da jirgi zai wuce, mutane da masu abubuwan hawan kan tsayana wani lokaci sai jirgin ya wuce, kafin kowa ya sami damar tsallaka wannan hanyar jirgi. Akan sami jerin gwanon jama'a, musamman idan jirgi bai hanzarta wucewa ba. A lokuta da dama mutane kan sami dokar dakatarwa, amma sai jirgi ya yi lattin wucewa kamar yadda ake zato. A wani lokaci kuma mutane kan sami wajen minti talatin suna jiran wucewar jirgi, wani abu da kan tayar da hankalin jama'a musamman ma'aikata da ke saurin zuwa aiki ko kuma masu wata lalura da ke buqatar gaggawar aiwatarwa, sai jiran wucewar jirgi ya kawo masu cikas. Haba, ba abin da ke qara baqantawa sai jiran wucewar jirgin Danqaro, wani irin jirgi mai tafiyar hawainiya da fitar hayaqi. Ba shi da sauri ko kaxan sai yawan ihu, da ke nuna ganinan tafe! Amma kafin ya zo ya wuce sai mutane sun zaqu. Haka dai mutanen Kaduna ke samun matsalar qetare *Railway Crossing* a wasu sassa na wannan gari.

Inda ake samun babbar matsala ita ce qetare kogin Kaduna akan gadar jirgi. A lokacin da ita ake amfani, da wannan gadar ita xaya qwal. Mutanen masu zuwa sabon garin doka ko masu zuwa Maqera daga Sabon Gari su kan sha wahala saboda hanyar jirgi ce ba ta mota ba. Amma a kan wannan gada hanyar mota da hanyar jirgi sun haxu. A wannan lokaci mutane na sintiri a kan wannan gadar, masu mota da babur da amalanke da basukur duk ita suke bi. Haka kuma masu shanu da awaki da raquma duk ita suke bi. Saboda haka idan ba a xauki tsauraran matakan tsaro ba, za a riqa yawan samun munanan haxura akan wannan gada. Domin motoci xauke da jama'a na iya yin karo da jirgi, wanda ka iya haifar da asarar rayuka masu yawa.

Domin hana aukuwar irin waxannan haxari, ya sa ma'aikatan Reluwe xaukar qwararan matakai da shimfixa dokokin bin hanya. A kan ce hanyar jirgi daban hanyar mota daban. Amma sai gashi dalilin rashin gadar mota, da jirgi da mota na bin kan kadarko guda xaya rak. To, da yake gadar jirgi ba a yi mata wani tanadin hanyar mota ba, saboda haka a kowane lokaci jirgi zai iya bin gadar ba tare da jiran kowa ba. A duk lokacin da zai wuce, sai a nuna alama ga jirgi nan tafe, a qalla da misalin rabin awa kafin zuwan na sa. Akan daxe ana jiran jirgi ya wuce, fiye da na *Railway Crossing*. A lokuta da dama akan shafe fiye da awa xaya ana

jiran wucewar jirgi, abin da ke sa jerin gwanon jama'a da motoci a titin motar da ke gavar kudanci da Arewacin kogin Kaduna.

A wani lokacin kuma idan mutane suka share tsawon lokaci suna jiran jirgi, ba za su ankara ba, sai su ga Aboqara ne zai wuce, xauke da heluma a zaune ko a shingixe. Idan zai wuce dafifin jama'a sai a hura usur da qarfi, wato alama ke nan da ke nuna wucewar Aboqara, saboda haka sai jama'a su hanzarta qetare gadar jirgi. Kaduna na qara bunqasa da jama'a, matsalar qetare kogi takan gada kuma na qara muni. An yi shekaru arba'in da shida jama'a na fama da wannan matsala.

To, mene ne zai sa a yi ta dakatar da mutane har su yi rabin sa'a tsaye alhali kuwa jirgi na can da nisa? Amma da yake harkokin ciniki suna ta qara buxuwa a sashen Kudu na qetaren kogin Kaduna, dakatarwa irin wannan ba ta kawo komai ba sai ta jawo qosawa da rashin jin daxin mazauna Kaduna a wannan lokaci. Sai da suka yi shekaru 46 cikin qosawa da rashin jin daxi, sannan sai da zuwan Gamji Allah Ya kawo masu qarshen wannan wahalar.

Kwaram! Sai ga shirin Sardauna na vunqasa masana'antu ya zo da niyyar kafa wasu masana'antu da kamfanoni a tsallaken gada, a sashen Maqera da Kakuri. Saboda akwai babbar illar rashin gadar mota da za ta sauqaqa zirga-zirga tsakanin kudanci da Arewacin Kaduna, shirin kafa masana'antu zai samu cikas sosai. Wannan dalili ne ya tilasta gina gadar mota, wadda zata sauqaqawa jama'a wahalhalun tafiye-tafiye tsakanin vangarorin wannan gari. An gina gadar mota a shekarar 1957. A halin yanzu kuma ana buqatar qarin wata gadar mota saboda qarin jama'a da motoci da ababen hawa. A shekarar 2007, wannan gada ta cika shekara hamsin saboda haka ya kamata a qara gina wa ta sabuwar gadar mota domin rage cunKwasan jama'a da rage tavarvArewar wannan tsohuwar gada. Idan aka samu gadar zuwa daban da ta dawowa, za a samu sauqin zirga-zirgan jama'a a tsakanin vangarorin wannan gari.

Firimiya Sir Ahmadu Bello ne ya buxe sabuwar kadarkon kogin Kaduna da aka gina ta akan fam dubu xari da ashirin da biyar (£125,000), kuma ya buxe gadar ce a ranar Laraba a gaban xinbin jama'a. A jawabin da ya yi na buxewa, Firimiyan ya ce yana so ya ya dinga tuna wannan kadarko a matsayin wata alama ta bunqasar ci gaban haxin kan yankin Arewa. Yana mai alfaharin cewa gadar ita ce irinta ta farko a matsayin wani gagarumin aikin ci gaba da aka aiwatar bisa umarnin zavavviyar Majalisar Dokoki.

Tunda farko Sardauna ya yi wa Ministan Ayyuka na Tarayya Alhaji Inuwa Wada marhabin, wanda ya zo domin shaida buxe gadar da kuma bin sahun dukkan wanda ke Kaduna wajen farin ciki da murnar-kammala wannan babba kuma muhimmiyar gada. Firimiyan yaci gaba da cewa. "A watan Yuli na shekarar 1921 wato fiye da shekaru 36 ke nan aka soma rubuta wasiqar koke a kan rashin gamsuwa da tsarin amfani da gadar jiragen qasa a matsayin titin mota. Daga nan aka ci gaba da samun waxannan 'yan koke-koke, qaruwar zirga-zirgar da aka

samu ta ababen hawa da ke tsallaken gadar a shekaru talatin da suka wuce sun sa dole a gina wata sabuwar gadar.

A shekarar 1952, ta qara bayyana a fili cewa idan zirga-zirgar ababen hawa ta qaru, za a shiga wani mawuyacin hali, inda a nan ne aka tsara gina babbar hanya ta yanki da ta tashi daga Kaduna zuwa Kachia da Keffi, kuma Sardauna da takwarorinsa suka soma hasashen bunqasar masana'antu a Kaduna ta Kudu. Ya ce:

> *Bayan shekaru huxu, inda wata qidaya da aka yi ta nuna a shekara ababen hawa da ke bin gadar a shekara sun kai xari shida da saba'in (670) sa'an nan qidaya ta baya-bayan nan ta nuna a duk rana ababen hawa a qalla guda dubu xaya da xari biyu da tamanin ke bin gadar a kullum, in sun bi da yawa kuma su kai su dubu biyu a kowacce rana.*[1]

Da ya juya ga ayyukan masana'antu da ke kankama a Kudu da kogin Kaduna kuwa, Firimiyan ya ce yana da muhimmancin gaske kada yankin Arewa ya tsaya ga tattarar ofisoshi da gidaje kawai, a'a ya zama cibiya ce ta kasuwanci da ke da muhimmanci ga yankin Arewa. "Gadar na xaya daga cikin hanyoyin da gwamnati na ta cimma hakan," inji Firimiya.[2]

Gamji ya buxe gadar motar kogin Kaduna ranar Laraba 2 ga watan Agusta na shekarar 1957. An gina wannan gada a kan kuxi fam 125,000. Ta na da tsawon qafa xari bakwai. Dalilai biyu suka sa yin gadar. Na farko dai, shi ne don rage wahalhalun zirga-zirga tsakanin Doka da Maqera, na biyu kuma saboda Masaqar Kaduna da ake son ginawa a wannan lokaci. To, tunda an samar da kadarko sai maganar kafa masana'antu ta taso gadangadan.

Masaqar Kaduna

Firimiyan Jihar Arewa, Mai girma Alhaji Sir Ahmadu, Sardaunan Sakkwato, shi ya aza harsashin ginin masaqan nan ta gwamnatin Jihar Arewa a Kaduna. Mutane da damasuka halarci wannan biki na aza harsashi. A ciki har da 'yan Majalisar Wakilai da kuma Darektocin kamfanin nan na Lancashire a Ingila da a ke kira David Whitehead and Sons Limited. Da su ne aka haxa gwiwa da gwamnatin Arewa wajen gina wannan masaqa.

Ita wannan masaqa za a gina ta daf da tashar jirgi ta Kaduna Jamsin. An ce in an gama ginin, za a fara aiki da injin-injin na saqa har guda xari uku. Allera ma kawai da za a fara da ita, dubu goma sha-huxu (14,000) ce!

---

1 NC, No. 522, 24/7/1957

2 NC, No. 522, 24/7/1957

An yi qasaitaccen taro a Kaduna Jamsin saboda shagalin aza harsashin ginin masaqar Kaduna. Dukan 'yan Majalisar Wakilai sun halarci wannan taro. Buga bisa qari ma takanas Kamfanin Saqan nan na Ingila da suka haxa gwiwa da gwamnatin Jihar Arewa ga kafa masaqan, suka turo nasu wakilan, don a yi wannan shagali da su.

A cikin jawabin da Firimiyan Jihar Arewa ya yi, ya ce yana matuqar farin ciki da Allah Ya sa a wannan rana zai aza tubalin harsashin wannan sabuwar masaqa a gaban shugaba da Daraktan masaqar kuma wakilan Majalisar Jihar Arewa.

Ya ce kamar yadda aka sani a cikin Qasar nan ana da wata qaramar masaqa, wadda waxansu qungiyar Jama'a suka kafa. Amma wannan ta bambanta da waccan, don a wannan za a yi amfani da audugar Jihar nan a kuma saqa kyallen da za su yi amfani da audugar qasar nan. To, cikin yardar Ubangiji za a sami biyan buqata a wanan wuri. Game da gama gwiwa ya ce:

> *Babban muhimmancin wannan masaqa shi ne ta gwada kyakkyawan zumunta da gama gwiwa a tsakanin cinikin qetare da albarkar qasarmu. Wannan gama kai an yi shi ne tsakanin. Hukumar Ciniki ta Jihar Arewa da Kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa da kuma Kamfanin David Whitehead na Manchester.*
>
> *Ran Litinin na zayyana nufin gwamnatin Jihar Arewa kan muhimmancin ajiyar kuxi a Jihar nan daga sana'o'in qetare. Har a cikin jawabina na ce, mun gane cewa lallai in muna son albarkar qasar nan ta ci gaba sosai har shekaru masu yawa, lallai za mu buqaci taimakon kuxi daga qetare. Muna maraba da wannan taimako, kuma muna marhabin da gogayya da zuzzurfan ilimi da ke tare da su. Shirye mu ke mu ba da gwargwadon taimakonmu ga kyautata ciniki tsakanin qwararrun sana'o'in qetare da na nan.*
>
> *Fatarmu ko yaushe, shi ne a irin waxannan wurare a ba 'yan Arewa damar samun hanyar shiga. A cikin wannan wurin, kamar yadda kuka ji, an yi shiri yadda mutanenmu za su samu halin koyo, don gaba su iya tafiya da wannan masaqa da kansu.*[1]

Firimiya ya qarasa da cewa, *"Ina roqon Allah Ya tabbatar da alheri a cikin wannan sha'ani tsakanin sana'o'in qetare da albarkar qasar nan. Allah Ubangiji ya sa albarka a cikin wannan sha'ani da zaman lafiya da farin ciki ga dukan ma'aikatan da su ke aiki a wurin nan, amin*."

---

[1] GTK 13/3/1956 shafi na 6

Yana gama jawabin sai ya aza harsashin ginin masaqar, ya ce,"Na tabbatar cewa wannan harsashin gini ya zauna dai-dai."

Mr. J.E Williams, Daraktan kuxi ya yi magana a madadin darektocin kamfanin. A ciki har ya ce, "Wannan yana cikin abin tunawa cikin zukatanmu na duniya. Bayan shekaru da dama na zamanku na al'adu, kunqudirta ku ci gaba wajen sana'o'i." A madadin kamfanin David Whitehead ya ce, "Muna alfahari da mutanen Jihar Arewa suka kira mu, 'yan Arewan Ingila, tun ma ba kamfaninmu ba da ke da qwarewar shekara xari da hamsin don su zo su taimake ku, su haxa gwiwa da ku kan wannan muhimmin abu."

A madadin kamfanin masaqar Kaduna da na David Whitehead sai Mr. Williams ya miqawa Firimiya kyautar dunqulen hauren giwa da azurfa don tunawa da wannan rana. Mr Fairclough, a madadin Taylor Woodrow (West Africa) Ltd., sumasun ba Firimiya kyautar wuqar gini ta a zurfa don samun zama lafiya. Ni da abokan aikina mun amince da mutanen Jihar Arewa. Hausawa su kance ba a xaukar kare ranar farauta"

Sardauna ya ce yana addu'a ainun a yi zave ba da firgitarwa ba, ba da tsoro ba, kuma lafiya lau."Ina roqon jama'ar Arewa su kwantad da hankalinsu a ranakun zaven nan. Ina roqon kowa da kowa ya ci gaba da sha'aninsa na zave.[1]

Wannan masaqa da za a kira Masaqar Kaduna "Kaduna Textile Industry", an kafa ta ne don saqa tufafi. Duka kuxin da za a kashe kanta zai kai fam zambar dubu da xari xaya, wato fam miliyan guda da dubu xari (£1,100.000). Su waxannan kuxi Hukumar Amfanin Gona da ta Raya Qasa na Jihar Arewa ne za su ba da biyu bisa uku, sulusin kuwa shi wannan kamfani na Ingila wato *David White head and Sons limited* zai cikasa.

Audugar Nijeriya ta Arewa ta na da kyau ainun, don haka a ke rububimta a kasuwar duniya. Da irinta ce ma masaqar za ta soma aiki. An ce a shekarun farko da soma saqan, za a iya yin kamar allera miliyan huxu. A sannu-sannu zai kai har allera miliyan goma sha-biyu. Wato in da abin a shimfixe su xai xai tsawonsa zai kai mil xari bakwai (700).

Kamfanin nan ta Lancashire zai zavo gwanayen Turawa su zo nan Kaduna su fara gwada ayyukan. Tun a wancan lokaci gwamnati ke niyyar aikawa da 'yan Arewa Turai don su qwarance irin aikin saqa. In sun dawo su amshi hannun waxannan Turawa. Idan aka gama masaqar, mutum xaruruka za su yi aiki cikinta.[2]

A lokacin da aka buxe Masaqar Kaduna tana da fiye da eka shida ginanna duk a qarqashin rufi guda, har ma ana iya cewa babu wani gini kamar wannan a duk

---

[1] GTK 13/3/1956 shafi na 6

[2] *Ibid*, 1956 shafi na 6

Nijeriya a wannan lokacin. Manufar wannan masaqa kuwa, ita ce su saqa zane, su yi saqa da audugar Nijeriya su maisheta akoko. Don saboda nasarar da aka samu, yanzu girmanta ya bunqasa sosai tana saqa tufafi iri-iri masu daraja.

Gwaggon Sarauniya *Princess Royal* aka shirya za ta buxe wannan masaqa, wadda kuma babu kamarta a Nijeriya, a lokacin da ta kawo ziyara Nijeriya. Ita ce ta buxe kwaleji ta 'yan mata ta Ilorin wadda ake kira da Turanci *Queen Elizabeth College*. An shirya da za ta buxe masaqar Kaduna, amma sai ba ta ji hanzari ba a wannan ranar don haka ba ta sami damar buxe wannan wurin ba sai Gamji ya yi bikin buxe masaqar.

Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardauna Sakkwato, ya buxe wannan masaqa a ranar 22 ga watan Nuwamba na shekarar 1957. Buxe wannan masaqa yana xaya daga cikin shirye-shiryensa na kyautata sana'o'i. Wannan wuri da aka keve a can sashen Kudu don yin masana'antu, sai sana'o'i ke samuwa. Irin waxannan wuraren yin sana'o'in, suna sama wa mutane ayyukan da za su yi. Dubban 'yan Arewa sun sami aiki, 'yan kasuwa da yawa kuma sun sami bunqasar arziqi ta hanyar wannan masaqa.

An riga an gina masaqa ta fam miliyan guda a Kaduna, wanda aikin yake na Nortex ne wani kamfani da ya gama gwiwa tare da wani kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa da kuma wani mai zuba jari na Sudan, Mr. E. Scroussi da kuma kamfanin Raya Qasa na Nijeriya. An kafa wannan haxin gwiwa a cikin watan Janairu na shekarar 1962, kuma Mr. Scroussi shi ne Manaja-Daraktan kamfanin. Shi kuwa kamfanin, a Kaduna ta Kudu yake kuma shi zai zama babba na biyu a Kaduna hedkwata.[1]

Qungiyar ma'aikatan masaqan Kaduna wadda ke wakiltar fiye da ma'aikata dubu biyu da xari biyar, ta yi wani taro a Kaduna. A taron qungiyar ne ta nuna damuwarta game da yadda waxansu Turawan masaqar masu duba ma'aikata waxanda ake kira, "Overlookers" suke qulla wani makirci da shugabannin ma'aikatar don korar waxansu ma'aikatan da suke koyon irin aikinsu, waxanda ake kira "Assistant Overlookers" don gudun ka da nan gaba su xauki muqamansu. Qungiyar ta cewai waxannan Turawa suna qulla makircin don korar ma'aikata waxanda ake sa ran za su goge su maye gurbin Turawa. Saboda haka sai Turawa suka tsane su. Hukumar masaqar kuma ta shiga basu gargaxi iri-iri da kuma tsoratasu da kora.[2]

Irin wannan hali ba ma'aikatan masaqa kawai ya shafa ba har ma da sauran wuraren aikin gwamnati da En'e inda ake son 'yan Arewa su qwarewajen aikin da suke koya daga baqi. Irin wannan qoqarin daqile 'yan Arewa har da Turawa a ciki. Abin da za a kira zagon qasa ga shirin "Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa." A

---

[1] GTK 13/3/1956 shafi na 6.

[2] *Ibid*. Maris 6, 1962.

qoqarin Sardauna na ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, ya baiwa ma'aikatu da masana'antu muhimmaci sosai. Saboda haka yake ziyarta wannan masaqa akai-akai, don yaji irin ci gaban da aka samu, ya kuma saurari matsalolin da suke addabar ma'aikatar da ma'aikatanta.

Firimiya Alhaji Ahmadu Sardauna ya ce "Masaqar nan ta Kaduna tana cikin abubuwan mamaki na Jihar Arewa." Firimiya ya yi wannan kalamine, a lokacin da yake kewaya sabuwar masaqan nan ta Kaduna. Sardauna ya yi sha'awar hanzarin da aka yi cikin gini da sauran abubuwan masaqar kamar su kafa injin-injin.Ya ce, "Ina farin ciki da na ga an cika alqawarin da aka yi mini, sa'ad da na ziyarci Manchester inda aka qulla yarjejeniyar kafa wannan masaqa.Wannan masaqa, kafata aiki ne wanda lallai ya dace gwamnatin Jihar Arewa ta yi alfahari da shi."

Firimiya yana tare da Alhaji Aliyu Makaman Bida, Ministan Ciniki da Sana'o'i na Jihar Arewa, da babban Sakataren Makaman Bida, Mr R.A Berrif,da Sakatarensa na Majalisa M. Audu Buba, da babban sakataren Ministan Sufuri na Nijeriya, Mr. H.M Varvell. Mr Fuller ne ya kewaya da Firimiya da 'yan rakiyarsa, ya ga ko'ina da ina cikin masaqar. An ce kafin Mr. Fuller ya zo nan Arewa,ya ma kafa irin wannan masaqa a qasar Rhodesia.

Firimiya ya ziyarci wurin da a ke nufin yin ma'aikatar yin Krola, wadda *Nigerian Breweries Limited* ke nufin ginawa,da waxansu qananan gidajen da Messrs D'Alberto and Bogialla-kamfanonin-'yan kwangila-ke ginawa,domin ma'aikatan masaqan nan. Firimiya ya ziyarci wurin ginin Majalisar shari'a wato "Kaduna Law Courts." Haka Sardauna ya riqa ziyarta masana'antu da kamfanoni akai-akai don ya bunqasa su, ya kuma qwarzanta ma'aikatansu.[1] Saboda haka ne ma wannan tagomashin masaqa ta bunqasa sosai har ta riqa saqa tufafi mai launi.

Don a inganta Masaqar Kaduna,an yi shirin yadda za a riqa yin turamen alawayyo da rinannun tufa a wannan masaqa.A cikin wannan shiri,har ma an ba da izinin kashe waxansu kuxi don tafiyar da aikin,don a sami damar yin alawayyo da rinannun tufa a wannan masaqa. An kashe qarin kuxi wajen fam dubu xari huxu da hamsin (£450,000). Wannan kuxi za a same su ne daga waxanda suka haxa gwiwa wajen kafa wannan masaqa wato Hukumar Ciniki ta Jihar Arewa da Kamfanin David Whitehead and sons (Nigeria) Ltd.

A wancan lokaci ma'aikatar masaqar na canjin aiki sau uku,sa'an nan ta na da Turawa talatin da biyar da 'yan Arewa xari bakwai da hamsin ke aiki a cikinta.A watan Yuli zuwa Agusta na shekarar 1959 aka qiyasce lokacin da za a gama sabon qarin ginin.

Mr. F. Fuller wanda yake kula da ginin masaqar,shi ne kuma yake kula da qarin ginin da aka yi. Ya ce ba zai manta da lokacin da Alhaji Aliyu Turakin

[1] GTK 12/2/1975

Zazzau,Shugaban Kamfanin Raya Qasa da Mr. R. A. Herrif, waxanda suke darktocin kamfanin suka ziyarci Hedkwatar *David Whitehead and Sons Ltd*, a Ingila ba, don su qara shirin buxa Masaqar Kaduna.

Nijeriya dai tana shigo da fiye da yadi miliyan xari biyu na tufan da aka saqa da auduga kowace shekara. Mafi yawan tufan da aka fi saqawa a wancan zamani, shi ne akoko,wanda ake sayarwa a Jihar Arewa. Saboda haka ne aka buxe wannan masaqa. An kuma qiyasce masaqar zata riqa saqa yadi miliyan goma sha-xaya zuwa goma sha-biyu kowace shekara,a wancan zamani kuwa,masaqar na saqa allera dubu goma sha-huxu da xari shida da injin na saqa guda xari takwas da tamanin da taqwas.[1] Tallar Masaqar Kaduna a Jarida:

MASAQAR KADUNA
Zata biya maka buqatun ka.
Ga akoko da alwayo mafi aminci daga masaqar da ta fi gwanancewa a nan Nijeriya-samakon qwarewa ainun, da kuma yin amfani da auduga mafi aminci da hanyoyi saqa na zamani ke nan. Ka na iya samun duk waxannan ta hannun shahararrun 'yan kasuwa masu harka da masaqa- da suka sani cewa "Kayayyakin Masaqar Kaduna" ba su da dama idan ana batun aminci. Don haka, nan gaba idan ka zo sayan Akoko ko Alawayo ka tabbata cewa daga "Masaqar Kaduna" suke… ZA KA SAMI MAFI DARAJA KAN KUXIN KA daga…

KADUNA TEXTILES LTD
(Kamfanin MASAQAR KADUNA)
KADUNA, NIGERIA –

Gidan rediyo da talabijin na taimakawa qwarai wajen yaxa ilimi da wayarda kan jama'a. Saboda haka Sardauna bai vata lokaci waje ginasu a Kaduna ba.

Gidan Rediyo da Talabijin na Kaduna

Gidan rediyo da talabijin na Kaduna wanda Gamji ya buxe da sunan *Broadcasting Company of Northern Nigeria*, (BCNN) an buxe wannan shahararren gida da qarfe shida (6.00 pm) na Yamma ranar 15 ga Maris na shekarar 1962. Wannan gidan Rediyo da Talabijin haxin gwiwa ne tsakanin gwamnatin Arewacin Nijeriya da Kamfanin "Granada Television" da "EMI." Wannan kamfanin rediyon ya fara watsa aikace-aikacensa da farko a xakin shawara, wato *Independence Hall* da ke Makarantar gwamnati ta Kaduna (wato Kaduna Government College). Ana watsa labarai da sauran ayyuka ta babbar tashar kamfanin da ke Jaji.

[1] *Ibid*., 23 Mayu 1958

A ranar 3 ga watan Agusta na shekarar 1963, babban gidan rediyo da talabijin ya komo gininsa na dindindin da ke titin Independence daura da titin Yakubu Gowon a yanzu. Zuwansa wannan wuri ya daxa bunqasa ayyukansa qwarai da gaske. Gani dai ya kori ji, amma gidan ya haxa-ji-da-gani ta hanyar watsa labarai ta rediyo, sannan kuma tare da watsa rahotanni domin kowa ya gani ta rediyo mai hoto wato talabijin.

Rediyo mai akwati wanda ake kira rediyon kwabo biyu saboda ana biyan sulai biyar a wata. Shi samfurin wannan rediyo an fi saninsa da *Radio Re-diffusion Service* da Turanci. Ya bambanta da samfurin rediyon da ake amfani da shi a yanzu. Rediyo mai akwati kamar tarho yake. Ana haxa shi da waya irin ta tarho don kama shirye-shiryen da ake watsawa daga gidan waya da ake kira *Post and Telecommunication* ko *P* and *T*. Daga wannan ma'aikata ake jawo waya zuwa gidajen da aka kafa. Haka kuma ya bambanta da rediyon da aka sani yanzu saboda shi wannan rediyon ba shida tashoshi sai guda xaya rak. Abin da mai rediyo zai iya shi ne qara sauti ko rage sauti kawai. Daga bisani ne aka qirqiro da "Wireless Radio," wato rediyo wanda ba a haxa shi da waya.

Ta waxannan hanyoyi biyu, gidan ya taimaka gaya wajen bunqasar garin Kaduna ba ma a Nijeriya kaxai ba a duniya baki xaya. Cikin 'yan shekaru qalilan sai gidan ya shahara wajen fahimtar da masu sauraronsa game da addininsu, da siyasa da kuma uwa-uba tsarin dokokin qasa. Shirye-shiryen rediyo mai hoto kuwa ya fi na kowane ban sha'awa tare da ilimantarwa. Ana watsa labarai da sauran shirye-shirye ta cikin harsunan Hausa da Ingilishi.

Tunda aka kafa wannan gidan rediyo da talabijin, an sami nagartattun ma'aikata da shugabanni daban-daban waxanda suka ba da taimako wajen bunqasa wannan gida. Irin kyakkyawan tsarin tafiyar da shirye-shirye daki-daki ba shi yiwuwa sai da qwararrun shugabanni da ma'aikata masu ilimi da basira tare da qwazo. Don haka shugaban wannan muhimmin gida, Alhaji Xahiru Modibbo ya cancanci yabo qwarai da gaske, saboda qwazonsa ne wannan gida ya bunqasa sosai. Sauran shugabanni waxanda suka taimaka wajen havaka wannan gidan rediyo su ne; Alhaji Abba Zoro, da Alhaji Sani Kwantagora da Muhammad Suleiman da Abdulkarim Albashir da Madam Martha Kande Audu wadda ita ce ta fara fitowa a rediyo mai hoto a cikin shekarar 1962.

Wajen fahimtar da jama'a game da abubuwan da suke faruwa na yau da kullum kuwa, ba za a manta da su Alhaji Adamu Salihu da Alhaji Lawal Yusufu Saulawa da Isa Abdulmumini ba, domin sun yi namijin qoqari a lokacin da qasar nan ke cikin bala'in yaqin basasa. A cikin shirinsu na wannan lokaci wato **duniyarmu A Yau**, sun bayyana wa duniya gaskiyar dalilan varkewar yaqin basasar tare da wargaza duk wata jita-jita da ke tasowa wadda ke barazana ga zaman lafiyar 'yan Nijeriya.

A wannan lokaci, sun taimaka wa 'yan Arewa wajen kwantar da hankalinsu. Ma'aikatansu sun sadaukar da kansu wajen wannan aiki, don haka har sun rasa Malam Buba Ciroma wani mai xauko masu labarai daga fagen-fama.

Wajen wayar da kan 'yan Arewa a wajen siyasa kuwa, ma'aikatan wannan gidan rediyo ba su da na biyu. A zamanin siyasa ta biyu kowa ya samu 'yancin faxin albarkacin bakinsa daga ko'ina birni da qauye na Arewacin Nijeriya. Shirinsu na Dandalin Siyasa da na Turanci wato *Democracy In Action* sun ilmantar da jama'a sosai, 'yan Arewa a wannan lokaci sun fahimci abin da ake nufi da siyasa. Akwai shirye-shirye masu qayatarwa da ilmantarwa waxanda ma'aikatanta na wannan gidan rediyo suka yi. Tarihin wannan gida ba zai manta da su:- James Audu da Abdulmalik Adi da Nyaka Mindapa da Shado Para ba. Sauran ma'aikatan da suka maido wa wannan gida wata martaba a Nahiyar Afirka baki xaya su ne:- Halilu Ahmed Getso da Lawal Musa Xangiwa. Siyasa tana xaya daga cikin dalilan da suka sa Gamji kafa wannan Gidan Rediyo da Talabijin, kuma waxannan qwararrun ma'aikata sun taimaka qwarai da gaske wajen yaxa siyasa.

To, duk inda gwarzo yake sai ya yi fama da maqiya. Bunqasar Rediyo Talabijin Kaduna a duniya baki xaya ya jawo mata maqiya daga Kudancin Nijeriya. Su waxannan maqiyan sun yi amfani da hanyoyi iri-iri don su tauye gidan rediyon. An yi yunqurin tauye tashar gidan rediyon don ta koma mai qarfin qaramin zango, amma abin yaci tura. An yi qoqarin yin wannan abu a lokacin gwamnatin Mulkin Soja qarqashin shugabancin, Janar Obasanjo, shirin bai yi nasara ba.

Rashin cimma burin maqiyan wannan gidan rediyon, ya faru ne saboda dalilai guda uku. Na farko kyakkyawan shugabanci da nagartattun ma'aikata da gidan ke taqama da su. Na biyu kuma amfanin da 'yan Arewa suka gani na wannan gida wanda zai kawo tunzuri muddin aka nemi tauye wannan gida ya zama mai qaramin zango, dalili na qarshe, shi ne manyan shugabanni da suka yi fito-na-fito da maqiyan gidan rediyon su.

Saboda haka ba za a manta da Malam Aminu Kano da gwamnan Kaduna na wannan lokaci ba, wato Guruf Keftin Usman Jibrin da Alhaji Isa Kaita da Alhaji Nuhu Bamalli don sun fito fili sun soki shirin. gwamnan Jihar Kaduna a wannan lokacin, ya tsaya-tsayin daka don ganin maqiyan wannan gida ba su ci nasara ba. Abin da ya yi wa Arewa, tarihi ba zai mance ba, ya nuna kishi da rashin tsoro ya kuma sadaukar da muqaminsa domin kishin Arewa. Dalilin yin haka ne ya sa aka yi masa ritaya. Ko da yake an raba shi da muqaminsa, amma wannan gwarzon xan kishin Arewa tarihi ba zai manta da rawar ganin da ya yi ba.

Daga baya wannan gidan Rediyo da Talabijin ya koma mallakar gwamnatin Tarayya, saboda haka aka canja sunansa zuwa "FRCN da NTA" wato *Federal Radio Corporation of Nigeria and National Television Authority*. Gamji ya kafa,

sun taimaka gaya wajen wayar da kan jama'a ta fannin da siyasa ko 'Daular Sardauna' kamar yadda shi Gamji ya yi nufi. Domin ya ce: "Kakan Ubana shi ya kafa Daular nan ta Sudan ta Yamma (wato Daular Usumaniyya). Ni kuma ga shi Sarkin Sarauta Allah Ya nufa zan yi babban taimako wajen kafa sabuwar daula ta jama'armu (wato Daular Sardauna). Kakan nan nawa an zave shi ya shugabanci runduna ta masu Jihadi don kafa daular nan tasa. Ni kuwa masu jefa quri'a ne suka zave ni don in yi taimako wajen gina qasa irin ta zamani."

Lallai Gamji ya yi namijin qoqari wajen gina qasa irin ta zamani, abubuwan da ya yi har yanzu sai bunqasa suke yi suna kuma buwaye Gidajen Rediyo da Jaridunsa sun tashi haiqan wajen yaxa Daular nan ta "Sardauna." Ita wannan daula wadda 'yan Kudu suka kira "Sardauna Empire" ta buwaya a Nijeriya. Saboda buwayar jamiyar NPC wadda Sardauna ke jagoranta ya haifar da mummunan juyin mulki da sojoji suka yi a watan Janairun shekarar 1966. Kamar yadda aka yi bayani sojoji sun angije Daular Sardauna ne saboda sun xauke ta wani garwashin wutar Daular Usumaniyya ce ke sake ruruwa a wannan zamani. Saboda haka suka kashe ta, a wani gagarumin martani ga Daular Usumaniyya da suka aiwatar, a ran 15 ga Janairun shekarar 1966.

Filin Wasa na Ahmadu Bello

Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato ya taimaka gaya wajen bunqasa wasanni a Arewacin Nijeriya, ta fannoni da yawa. Ya kuma taimaka wajen kafa qungiyoyin wasanni iri-iri domin havaka wasanni da qara danqon zumuncin 'yan Arewa. Misali, kamar qungiyar wasanni na Arewa wato *Northern Sports Association* wadda aka kafa ta a qarqashin shugabancin Alhaji Ahmadu Xanwawu a cikin shekarar 1957 da takwarar ta wato *Northern Nigerian Sports Commission*. Waxannan qungiyoyi sun taimaka qwarai da gaske wajen raya wasanni a Nijeriya ta Arewa

Shi Gamji Allah Ya yi shi mutum ne ma'abucin wasanni tun yana xan makaranta yake da sha'awar yin wasanni iri-iri kamar wasan 'Fives' da qwallon Gora. Wasanni na sada zumunci, fahimtar wannan ta sanya Gamji ya gayyato 'yan wasan qwallon 'Fives' na Kwalejin "Eton" ta Ingila domin su zo su yi wasan sada zumunci da takwarorinsu 'yan Arewa a shekarar 1964. Gamji ya yi shirin aika wa da 'yan wasan 'Fives' na Arewa zuwa Ingila, sai Allah Ya yi masa rasuwa a shekarar 1966. Amma Manjo Hassan Usman Katsina, tsohon gwamnan Jihar Arewa a wannan lokaci, ya. aika da 'yan wasan qarqashin shugabancin Alhaji Mamman Lagos.

Ban da qungiyoyi da Gamji ya kafa don bunqasa wasanni, ya bayar da kyautar kofin Zinari don qara bunqasa wasanni, ba wajen wasan qwallo ba ma a'a har da gasar sukuwar dawaki. Shi kansa yana da dawakan sukuwa, a shekarar 1960 ya ba

da kyautar kofin Zinari wato *Northern Derby* don bunqasa wasan sukuwa da sauransu.

Amma babban taimakon da Gamji ya yi wa Arewa shi ne, gina makeken filin wasa a garin Kaduna. Wannan filin wasa na zamani da ya gina, an sanya masa sunansa, wato Filin Wasa na Ahmadu Bello don tunawa da muhimman abubuwan da ya yi don bunqasa wasanni a Arewacin Nijeriya. Gamji ya buxe filin wasan, ranar 2 ga watan Agusta a shekarar 1964, an kashe Fam miliyan xaya wajen ginin wannan makeken filin wasa. Gidan wasan na qarqashin shugabancin Alhaji Mamman Lagos wanda yake shi ne Janar-Manajan filin wasan.

Filin wasan na Ahmadu Bello, an gina shi a fili mai faxin e'ka xari da talatin (130), inda zai xauki mutane fiye da dubu talatin. Akwai wuraren wasa iri-iri kamar su guje-guje da tsalle-tsalle, da qwallon qafa, da na tenis, da wasan dambe da kwangirin gasar ninqaya irin na zamani wanda aka gina kwanan nan. Akwai kuma wuraren sheqe aya da sauransu. Ana amfani da wannan gida wajen bukukuwa da taron jama'a na addini ko wasannin al'adun gargajiya.

Mai martaba Sir Ahmadu Bello, ya ziyarci filin wasa na Kaduna wato Ahmadu Bello Stadium, don ya duba ci gaban ginin da ake yi. Wannan gidan wasa za a kashe kuxi fam dubu xari takwas da hamsin (£850,000) wajen gininsa. Cikin waxanda suka raka Sir Ahmadu Bello, har da Ministan Ayyuka na Jihar Arewa, Alhaji Usman, Sarkin Maska; da Alhaji Muhammadu Bashar Wamban Daura, Ministan Tsara Arziqin Qasa da kuma Alhaji Ibrahima Biu, Ministan Watsa Labarai na Jihar Arewa.

A lokacin da suka ziyarci filin, Sakataren Ministan Ayyuka, Mr. E Jones shi ne ya zagaya da su. A qarshen ziyararsu kuma, Sir Ahmadu Bello ya bayyana cewa haqiqa aikin ya yi kyau kuma an yi aikin sosai.[1]

Mai martaba da girma Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato ya samo wa Nijeriya, musamman Arewa, abubuwan raya qasa da jin daxin jama'a saboda haka ya kamata su yi alfahari da shi, su qara nuna godiyarsu ga Ubangiji da ya yi musu baiwa da Sardauna. Irin jawabin da Sardaunan Sakkwato ya yi a wurin buxe filin wasanni na Ahmadu Bello a Kaduna, jawabi ne da ke qara nuna Sardauna tauraro ne da ke haskaka qasar nan ba tare da nuna bambancin komai ba. Arewa na alfahari da Ahmadu.

An yi bikin buxe babban Filin Wasan Ahmadu Bello a Kaduna, a ranar 2 ga watan Agustan shekarar 1964, ana kuma sheqa ruwan sama a lokacin. A lokacin da aka yi bikin buxe wannan Fili, akwai 'yan kallo kamar miliyan xaya suka hallar a wajen shagalin bikin, kuma Mai martaba Alhaji Ahmadu Bello Sardauna, shi ne da kansa ya buxe filin. Manyan baqi da yawa daga kowane sashin Jamhuriya sun

[1] GTK 1146, Jumma'a 24/1/64

halarci bikin buxewar, ban da dubban mutane waxanda suka yi kallon sha'anin a gidajen su ta cikin rediyo mai hoto.

Dubban mutanen da ba su kula da ruwan sama da ake yi ba a lokacin, sun ji lokacin da Sir Ahmadu Bello ya cewannan shi ne farkon shigowar sabon zamani na wasanni a Nijeriya ta Arewa. An sha yi wa Sardauna guxa a lokacin da yake jawabin buxe filin, wannan kuwa ya nuna cewa babu shakka Arewa ta yi niyyar zama jagorar sauran Jamhuriya wajen sha'anin wasanni.

An soma wannan biki ne a lokacin da Firimiya ya iso filin cikin buxaxxiyar mota, bayan ya ratsa babban fili da dubban mutane suka yi layi suna yi masa kirari har ya iso filin inda ba masaqa tsinke don yawan mutane, kuma baki xaya suka tashi suka yi gaisuwa ta barka da zuwa, jama'a sun yi masa jinjina na nuna so da qauna. Dubban mutane sun jiqe sharkaf saboda ruwan sama da ake yi, Sardauna na ma a wata lema ya iso tsakiyar filin.

Ministan Tsimi da Tanadi, Mai girma Alhaji Umaru Vavura, Sarkin Fulanin Ja'idawa, wanda ma'aikatarsa ce ke xauke da alhakkin sha'anin wasanni, shiya karvi Firimiya a sa'ad da ya iso filin. Duk da ruwan sama da ke dukkan jama'a amma kowa ne mutum na cikin farin ciki da alfahari da wannan rana mai ximbin tarihi. An qare bikin buxe filin sa'ad da Firimiya ya yanke wani xan qyalle a tsakiyar filin bayan da ya gama jawabinsa na buxewa.

Da maraicen Lahadi, kuma mutane masu ximbin yawa sun yi kallon wasan qwallon qafa wanda aka shirya musamman don wannan rana, tsakanin 'yan wasan *Arewa Northern Lions* da waxansu gwanayen wasa na Ingila da ake kira *Queen's Park*.

Mutum fiye da dubu talatin (30,000) suka riqa yi wa 'yan wasan Ingila kirari sa'ad da suka yi nasara a karon da suka yi da 'yan wasan qwallon qafa na Arewa a shagalin buxe Filin Wasa na Ahmadu Bello, wanda aka kashe fiye da fam miliyan guda wajen gina shi.

Manyan baqin da suka halarci kallon wannan wasa sun haxa da gwamnan Arewa, Mai girma Alhaji Sir Kashim Ibrahim wanda shi ne Babban Baqo cikin 'yan kallo. Mai martaba Firimiya da kansa ya halarta tare da Ministocin gwamnatin Tarayya da na Jihohi, da qananan Ministoci, manyan Sarakuna da shugaban Ma'aikatar Taba, Mr. Walton-Wooley, wanda kamfaninsa ne suka xauki xawainiyar shirya komai da komai game da wasan.

Wannan wasa kam sai wanda ya gani, domin ba a tava yin kamarsa ba a duk Arewa, kuma su *Queen's Park* nan na Ingila sun nuna, gwaninta matuqa wanda ya jawo musu yabo daga wajen 'Yan kallo. 'yan wasan Ingila, sun nuna suna da haxa kai qwarai ko da yake da aka soma wasa *Northern Lions* sun tsaida su, sun hana su damar zuwa gidansu.

An yi kamar minta goma sha-biyar ana ta xauki da daxi, abin da ban sha'awa ainun yadda 'yan wasan Ingila ke mallakar qwallo. A wani lokacin, an zaci

Northern Lions ce za ta yi nasara, ko kuma a tashi canjaras amma wannan sai ya kau a sa'ad da 'yan wasan *Queen's Park* suka sami damar keta dangan kariyar 'yan Arewa. Wani kururuwa da aka yi wa 'yan wasan Ingila, har ya sa qasa ta girgiza, saboda ihun da dubban 'yan kallo suka yi suka yi baki xaya, sa'ad da wani daga 'yan *Queen's Park* wai shi Miller ya varke da gudu ya kaucewa kariya biyu na Arewa a jere, ya zunduma qwallo ta shiga cikin ragar gidan 'yan Arewa. Abin ya zama kamar walqiya, har duk da gwanintar Rigogo mai tsaron gidan Arewa, ya kasa tare qwallon. Wannan shi ne ci na farko.

Wannan ci na farko ya sa wasan ya daxa zafi. Kowane sashi sai qoqari yake yi don yaci qwallo. A kai can, a komo nan, kai, abin ba dama. Don kuwa abin sai wanda ya gani. An tashi wasa cikin farin ciki da annashuwa, 'yan wasan *Queens Park Rangers* sun yi nasara da ci uku ba ko xaya (3-0).

Filin Wasa na Ahmadu Bello ya taimaka sosai wajen bunqasa wasanni, ba a Arewa kawai ba duk faxin Nijeriya baki xaya. Filin kuma ya qara qayatar da garin Kaduna, kusan kowanne qarshen mako sai garin ya qaru da baqin jama'a waxanda su kan zo daga garuruwa daban-daban na Nijeriya ko qasashen waje, don kallon wasa wanda a kan yi da daddare ko da rana. Akwai kumafitilu na zamani waxanda a kan kunna su lokacin da za a yi wani wasan da dare.

Jaridar *New Nigerian*

A shekarar 1939 aka kafa jaridar Gaskiya Ta fi Kwabo (GTK) wanda mashahurin mutumin nan Alhaji Dr. Abubakar Imam ya zama Editan ta na farko. An kafa tane domin ta taimakawa wajen wayar da kan jama'a akan yaqin Hitler wanda ya varke a wannan shekara. Wannan jarida ta taimaka gaya wajen bunqasar ilimi da wayewar kan jama'a a harkokin siyasa da havakkad da al'adu da xabi'un 'yan Arewa. An kuma sami shekaru masu tsawo babu wata jarida a Arewa, sai GTK.

Ranar 1 ga watan Janairun shekarar 1966, Gamji ya kafa wannan gidan Jaridar *New Nigerian* wadda ba ta da na biyu wajen kwarjini da bunqasa a wannan zamani. A wannan rana ce marigayi Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato ya yi kira da babbar murya ga ma'aikatan wannan jarida da su faxi gaskiya a duk al'amarinsu domin gaskiya babbar makami ce.

Ma'aikatan wannan babbar jarida tun a wannan rana mai muhimmanci suka lashi takobin faxin gaskiya komai xacinta a ko'ina cikin kuma kowane hali. Wannan ita ce maqasudin bunqasa da kwarjininta a yanzu. Sauran abubuwan da Gamji ya yi masu wasiyya da su yi shi ne, bai wa duniya labaru game da Arewa, haka kuma xauko labarun duniya domin amfanin 'yan Arewa. Bayan mako biyu da barin waxannan wasiyyoyi ne Gamji ya yi shahada.

A ko'ina a duniya kowa ya san waxannan jaridu waxanda suka qunshi *Sunday New Nigerian* on Sunday, wato jaridar *New Nigerian* ta ranar Lahadi, da Gaskiya

Ta Fi Kwabo da *New Nigerian* a yanzu. Wannan jarida ta taka rawar gani wajen fahimtar da duniya al'amuran duniya ga 'yan Arewa, haka kuma ta yadda duniya ta yi wa Arewa kyakkyawan sani ba domin komai ba sai domin taimakon wannan Jarida. A yanzu ma aikinta ya buwaya ba a Arewa ba a duk sassan wannan qasa na amfana da ita.

Kyakkyawan riqon wasiyyoyin Gamji da wannan jarida ta yi tare da bunqasarta sun yiwu ne saboda qwararrun shugabanni da ma'aikata da Allah Ya bai wa Jaridar ta *New Nigerian* xin. Saboda haka tarihi ba zai manta da Manajin Darakta na farko, Mista Charles Sharp da Malam Adamu Ciroma Editanta na farko (a 'yan qasa) da Malam Mamman Daura da Malam Turi Muhammad da Marigayi Rasaki Aremu, saboda su ne ginshiqan bunqasar wannan jarida. Da yawa daga cikinsu sun sha xauri ba domin komai ba sai domin gaskiyar al'amarinsu. Bunqasar wannan jarida ya nuna gaskiyar wasiyyar Gamji"Gaskiya babbar makami ce."

Babban Asibitin Kaduna

A watan Janairu na shekarar 1961 ne gwamnatin Jihar Arewa ta bayyana niyyarta ta gina Babban Asibiti a garin Kaduna Hedkwata domin a wannan lokaci an qiyasta garin nada yawan jama'a kamar dubu arba'in da uku (43,000). Shi wannan Babban Asibiti da za a xanxara zai zama gini ne na zamani.

In an gama ginin wannan asibiti, za a sami gadajen kwanciyar marasa lafiya har xari shida da takwas. Tirqashi, lallai gwamnatin Sardauna na shirin gawurtaccen aikin taimakon jama'ar Kaduna da Arewa baki xaya[1] gwamnatin Firimiya ta a faxa a cika ce. Saboda haka sai akasa ranar bikin aza harsashin wannan muhimmin asibiti. Kafin kace kwabo har an gama gina shi. Ba tare da vata lokaci ba sai maganar buxe wannan asibiti ta zo a dai-dai lokaci.

Sardauna ya buxe sabon babban Asibitin Kaduna wanda aka kashe fam dubu xari takwas (£800,000) wajen gininsa. A bikin da aka yi na buxe asibitin, ko da yake qaramin biki ne, duk da haka ya qayatar ainun.

Mai martaba wanda Ministoci uku suka raka shi don wannan rangadi nasa, ya nuna farin cikinsa ainun a ranar buxe wannan asibiti na Kaduna, domin ko ta shigar da ya yi ta fararen kaya ma kawai ana iya gane haka. A jawabinsa da ya yi na gabatarda Mai martaba, Ministan Lafiya Dujiman Barno, ya bayyana cewa bai daxe ba da hawa wannan sabon matsayin nasa na ministan Lafiya,saboda haka duk jawabinsa zai yi a madadin waxanda ya gaje su ne wato Alhaji Ahman Patagi, da Alhaji Ahmadu Fatika, Sarkin Fadan Zazzau, waxanda su ne su ka yi aiki tuquru don tabbatadda wannan sabon Asibiti.

---

[1] GTK 20 ga Janairu 1961, shafi na 9.

Ya ce tun cikin 1960 aka fara shirin gina wannan asibiti, amma saboda waxansu dalilai masu nauyi, dole abin ya yi jin, amma da yake dole a san abin yi domin qaruwar jama'a, sai aka yi ta shawarwari da dama, har dai aka dai-daita tsayad da gina wannan sabon asibiti wanda amfaninsa zai yaxu zuwa ko'ina a Nijeriya ta Arewa. Saboda haka aka shirya wannan sabon asibiti mai gadaje xari biyu da *arba'in* (240) don ya zama makwafin Tsohon Asibiti mai gadaje xari da saba'in da takwas (178). Ya bayyana cewa wajibi ne ya godewa ministan da waxanda su ka yi wannan qasaitaccen aiki, kuma wajibi ne ya godewa wanda ya zayyana sabon asibitin shi da waxanda suka yi aikin wurin wato kamfanin D'Alberto, da Bogialla hoydens da T.C.N.

Ministan ya ce saboda yawan mutane da ke ta qaruwa a Kaduna an ga ko kaxan bai kamata a rufe tsohowar asibiti ba, domin samuwar wannan sabon asibiti ba, saboda haka za a ci gaba da yin amfani da tsohon. Shi sabon asibitin zai kasance domin masu karvar magani ne na mata masu ciki da yara 'yan qananan yara marasa lafiya da kuma warkad da masu fama da ciwon ido, shi kuwa tsohon zai kasance domin masu kwanciya da kuma masu cuce-cuce da ake iya xaukarsu. Daga nan ne dai Minista ya roqi Mai martaba ya buxe sabon asibitin. Mai martaba Alhaji Sir Ahamadu Bello, kafin ya buxe wannan sabon asibiti, sai da ya yi dogon jawabi ya ce:

Assalamu Alaikum Ministoci, manyan baqi maza da mata kamar yadda Ministan Lafiya ya bayyana ne, cewa wannan taro ba taron bikin buxe wannan sabon asibiti ba ne kawai, taro ne na saduwa da tsofaffin abokai, amintattu. Ina kuwa farin ciki ainun da Allah Ubangiji Ya bani ikon zuwa wannan sabon asibiti har gashi ina tare da ku a yanzu. Ina kuma cike da farin ciki tare da godiya mai yawa saboda darajanta ni da Ministan lafiya ya yi, har ya roqe ni in zo im buxe wannan sabon asibiti.

Ministan dai ya bayyana maku irin wahalar da aka sha kafin a gina wannan asibiti. Abin godiya ne kuwa babba da ga shi Allah Ya kawo mu ranar ganin kyaun abin da muka shuka. Wato zuwan ranar ganin qarewa wannan kyakkyawan gini mai ban sha'awa da taimako. Wannan sabon asibiti, ba wurin warkad cuce-cuce ne kawai ba, wurin horar da Ungozomomi, ne kuma za a riqa horar da likitocimmu masu tasowa don amfanin Jiharmu.

Haka kuma ba asibiti ne ba na mutanen Kaduna kawai, har ma da waxanda ba a Kaduna suke ba, su ma za su amfana da wannan asibiti, domin suna iya zuwa neman taimako. Kamar yadda asibitin Kano ke da qwararrun gaske, kuma ya zama ba shi da na xaya, to, haka nan ma wannan sabon asibiti, shi ma zai kasance muqamin kamar iri guda ne

da na Kano, za mu kasance muna da wurare biyu ke nan, Kano da Kaduna.[1]

Bayan haka sai Mai martaba ya juya bisa tsohon aikin alqawarinsa inda, ya bayyana cewa burinsa ne ya ga an gina asibiti a kowane wurin zave na Jihar Arewa, amma da yake wannan ba qaramin aiki bane, kuma aiki da kuxi abu ne mai wuya, dole a yi komai hankali, cikin natsuwa. Ya ce yana fatan Allah zai yi mana tsawon rai. Da za mu ga ranar cika wannan alqawari na yin asibitoci a kowace mazava.[2]

Da ya juyo wajen ma'aikatan wurin, Mai martaba ya gargaxe su da su yi aikinsu *fi sabilillahi* ba tare da son zuciya ko ha'inci ba. Ya ce tun da yake su suka sa ransu ga yin wannan aiki na taimako, to, lallai ne kuwa su fidda kowane irin ha'inci da ke ransu. Ya ce akwai waxansu waxanda ba za su himmatu ba, sun gwammace bin hanyar abokansu manya don neman taimako ko kuma su nemi hanyar yin kuxi cikin sauqi,to, masu yin wannan abin kunya, duk wanda aka same shi da irin wannan mummunan hali, ko kaxan ba za a raga masa ba.

A qarshen jawabinsa, Mai martaba ya jawo hankalin mutane kan su kula da lafiyarsu. Ya ce akwai mu da tsohon karin maganar da ke cewa, " Rigakafi ya fi magana", to, wannan kuwa karin magana ne mai ma'ana da gaske kuma ba ana nufin komai ba ne, ana nufin mu tsare lafiyarmu ne. Saboda haka sai mu qara kula ainun wajen tsare lafiyarmu.

Sardauna ya ce yana roqon kowannenmu wanda yaji wannan magana da wanda ya yi wannan magana da wanda ya karanta ya qara mayar da hankali ainun wajen sha'anin tsabta. A kula da qananan yara kada afita harkarsu domin ganin qanqartarsu. Da zarar mutum ya kamu da rashin lafiya, komai qanqartar ta, to, ya hanzarta zuwa wurin neman magani. In 'yan yara ba su da lafiya, a hanzarta kai su wurin magani, haka kuma iyaye. Idan an lura da haka, to ba shakka yawan rashin lafiya zai yi sauqi kuma waxanda ke kwance a asibiti yanzu, da sun kiyaye yin haka, da ba su kai ga haka ba. Daga nan ne fa Minista shi da Babban Sakatarensa suka yi ta bi suna nuna wa Firimiya wurare dabam daban, wuraren da suka ba kowa sha'awa bisa yadda aka tsarasu.[3]

Gamji ya buxe wannan babban Asibiti mafi girma a Arewa a wannan zamani, a ranar 17 ga watan Mayu na shekarar 1965. Asibitin na da gadaje masu yawan gaske kimanin xar biyu da arba'in (240) kuma tsohon asibiti mai gadaje xari da

---

1 GTK 20 ga Janairu, 1961, shafi na 9

2 *Ibid.*

3 GTK 20 ga Janairu, 1961, shafi na 9

sittin da takwas (168) na qarqashinsa ne. An kashe fam miliyan biyu wajen gina wannan sabon asibiti irin na zamani.

Asibitin nada likitoci masana cututtuka iri-iri da masu aikin fixa. Shi ne yanzu Asibitin koyarwa da ke qarqashin Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariya. A nan ake horar da likitoci da Unguwar-zoma da masu kula da majinyata. A harabar asibitin kuma Gamji ya buxe Asibitin Idanu wato *Guiness Eye Clinic* a ranar 13 ga watan Fabrairu a shekarar 1962.

Asalin tsohon Asibitin mai gadaje xari da sittin da takwas (168) an gina shi domin jama'ar Sabon Garin Doka ne. A wannan lokacin kuma Asibitin Turawa shi ne "St. Christopher's Church" da ke titin Sakkwato a yanzu. Babu ruwan mutanen Doka da wannan Asibiti sai Turawa.

A lokacin da Gamji ya zo sai ya fahimci cewa asibitin jama'ar Sabon Gari ya yi qanqanta qwarai da gasken-gaske, don haka sai ya yi hanzarin faxaxa shi. Amma na Turawa kuwa, tun cikin shekarar 1938 suka faxaxa nasu, a lokacin da suka gina Asibitin *Nursing Home*. Turawa ne kawai ke amfani da wannan asibiti har zamani mai tsawo. Baqar fatar da ya fara kwanciya a wannan Asibitin Turawa shi ne wani mutumin Saliyo mai suna Mista Johnson.

Makarantar Batinariya

A ranar Juma'a 25 ga watan Maris na shekarar 1960 Mai girma Firimiyan Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello ya yi bikin buxe makarantar Batinari da ya gina akan titin Mando da ke kusa da Kaduna, inda aka kashe fam dubu saba'in da biyar (£75,000) wajen ginata. A wannan rana Sardauna ya bayyana dalilin gina Makarantar, mai suna *Investigation and Veterinary Training Centre*, a gaban xaruruwan mutane da manyan baqin da suka halarci wannan biki.

A jawabinsa Firimiya ya ce ita wannan cibiya an buxe ta ne saboda a qara lura da cututtukan gaji, da aka kuma aza harsashi mai qarfi na kula da riba da havakar masana'antar kaji a Arewa. Sir Ahmadu Bello ya qara da cewa amfanin dabbobin kiwo a nan gaba a Arewa, abu ne da kowa ya sani. Jihar Arewa ce ke samarwa jama'arta isasshen nama sa'anan ta aika da shanu dubu xari uku da hamsin (350,000) zuwa ga sauran jihohi da hedkwata Qasar nan tare da dubban tumaki da awaki.

Sardauna ya nuna godiyarsa ga Hukumar Raya Qasa ta Jihar Arewa wadda itace ta ba da isassun kuxin da'aka gina wanan makaranta, da kayayyakin aiki da xakin binciki tare da ma'aikata, da kuma agajin qasar Amirka ta qungiyar *International Cooperation Administration* (ICA) wadda ta xauki nauyin horar da da ma'aikata.

Ya ce ita wannan *Veterinary School* tana da kyau kamar kowacce take kamarta a Afirka. An gina ta ne domin ta zama qari ga horon da ake samu a

Makarantar Binciken Ciwon Dabbobi a Vom wadda take qarqashin Hukumar Tarayya.

Makarantar Vom za ta ci gaba ne da horar da da 'yan Sakandare, ita kuma wannan makarantar Mando ta riqa bayar da qananan horo ga ma'aikatan En'e waxanda ke da ilimin Firamare. Amma horar da da ma'aikata bai tsaya akan karatu ba, har ma akwai horon da ake bayarwa a xakin bincike wato laboratory. Ana kuma ba da Kwas ga 'yan Arewa domin su sami damar qara ilimi a fannin bincike (investigation) da nazarin (research) cutuuttukan dabbobi.

Sardauna ya ce yana sane da shirin da kwamitin, *Technical Cooperation in Africa South of the Sahara* (CCTA) ke da shi na wajen taron Kwas na duniya akan kaji, wato *International Poultry Course*, da za su yi a shekara mai zuwa. Maqasudin yin wannan taro shi ne don a horar da ma'aikata cutuuttukan kaji da maganinsu, domin sauran qasashen Yammacin Afrika. Shi wannan taro zai qara faxaxa hanyoyin da ake amfani da su a qauyuka.

Ya kuma ce yana farin ciki da cewa xan bincike na wannan cibiya ya dace da na duniya wajen koyarwa da ba da babbar diploma ta sana'a ga ma'aikata da suka kammala karatu a wannan makaranta.

Daga qarshe sai Sir Ahmadu Bello ya yaye labulen da ke nuna alamar buxe wannan makaranta. Sa'an nan aka shigarda shi harabar makarantar, inda ya duba azuzuwa, xakunan bincike da wajen qyanqyasar kaji harda xakunan xalibai.

A cikin waxanda suka halarci wannan biki harda Ministan Dabbobi da Gandun Daji, Alhaji Abdullahi Xan Buram Jada, da Mr. G. Lorimer, Babban Sakatare Mai riqo, da Dr. S.G. Wilson, babban jami'i mai kula da sashen nazari; da Mr. D.E Macgregor, shugaban sashen ayyukan waje, da kakakin Majalisa Alhaji Umaru Gwandu, da Sakatororin Falimantare, da Mr. C.J. Quinlan, Qaramin Jakadan Amirka na yankin Arewa, da kuma kantoman Kaduna Mr. R.G. Adams.[1]

Babbar Kotun Arewa

Babban Kotu a lokacin mulkin Turawa, an gina ta a cikin shekarar 1920 (tana nan a farkon titin Ibrahim Taiwo kusa da Gidan Yari). A kusa da wannan kotu akwai Ofishin Kantoma da ofishin 'yan Sanda na farko duk a zamanin Turawa. A wannan kotu ce ake zuwa daga ko'ina na sassan Arewa don xaukaka qara. Amma saboda bunqasar garin Kaduna da Arewa baki xaya sai ya zama wajibi a kafa babbar kotu a wannan gari, abin da bai samu ba sai a zamanin Gamji.

A cikin watan Agusta na shekarar 1957 aka fara ginin sabuwar babbar kotu, an gama aikinta a cikin shekarar 1959. gwamnan Jihar Arewa na wannan lokaci, Sir Gawain Bell shi ya yi bikin buxe ginin a ranar 5 ga watan Nuwamba na shekatar 1959.

[1] The Nigerian Citizen, Asabar March 26. 1960

Sir Gawain Bell, gwamnan Jihar Arewa ne ya buxe sabuwar Kotun Jihar Arewa, wadda a wajen gina ta aka kashe fam dubu xari biyu da saba'in da biyu (£272,000). An yi bikin buxe kotun a ranar Alhamis, 5 ga watan Nuwamban shekarar 1959, a wani qasaitaccen bikin da Sarakuna, da Shugabanni, da Ministoci, da Lauyoyi, da Jama'a masu ximbin yawa suka halarta.

Kafin ya buxe ginin, sai da gwamnan ya dubi faretin bangirma da 'yan Sandan En'e qarqashin jagorancin *Superitendant* xin 'yan Sandan Malam Baba Jimeta, a lokacin da 'yan budujalan ke kaxe-kaxe da bushe-bushe. Daga nan sai Mr. George Ohikere, Ministan Ayyuka na Jihar Arewa ya gabatar da Mai girma Gwamna ga manyan baqi. Yana gamawa sai Malam Junaidu, Wazirin Sakkwato, da Reverend Davies suka buxe taron da addu'a.

Ana gama addu'a sai Mr. Ohikere ya miqa wa Mai girma mabuxan azurfa, wanda da shi ne Gwamna ya buxe sabon ginin Kotun. Yana buxe kotun, sai Cifjojin Jihar Arewa, Sir Algernon Brown ya jagoranci Gwamna da manyan baqi zuwa cikin wannan babbar kotu, a inda ya nuna masu wurare daban-daban. Ana nuna wa manyan baqin farfajiyar wannan gini da babban Ofishin Cif jojin Jihar Arewa, daga bisani da suka kammala duba wuraren, sai Gwamna, da Firimiya, da Cifjoji suka hau kan kujerunsu, da ke dandamalin manyan baqi, inda suka gabatar da jawabinsu.

Cif-joji ne ya fara jawabinsa, ya ce yana matuqar farin ciki da maraba da baqi zuwa wannan kotu, wadda ya yi imani da za a iya kamanta ta da duk wata kotu da ke Hedkwatar wata qasa a duniya. Sir Algernon Brown, ya nuna godiyarsa ga ma'aikatan Ma'aikatar Ayyuka waxanda suka zana suka kuma gina wannan babbar kotu, qarqashin shugabancin Ministan Ayyuka. Ya ce babban abin qayatarwa a wannan rana shi ne haxin gwiwar vangarorin shari'a, a inda Hukumar shari'a ta musulunci da Babbar Kotun Jiha za su zauna a gini guda, in an kammala gyara, harkokin shari'a da ake yi yanzu, wanda kuma za a kammala a tsakiyar shekara mai zuwa. Ya cewaxannan gyare-gyaren suna nuna wani sabon falle ne a harkar sharia a wannan jiha. Wannan tsari ne wanda wasu manyan qasashen Musulmin duniya ke amfani da shi, kuma tsari ne da ya samu qarvuwa a duniya baki xaya saboda yana tabbatar da haqqin xan-Adam.

Malam Junaidu, Wazirin Sakkwato a nashi jawabin cewa ya yi, ya goyi bayan abin da Cifjoji fa faxa a jawabinsa. Ya ce a matsayinsa na mai ba da shawara a kan harkokin musulunci ga Majalisar Sarakuna da kuma matsayinsa na Shugaban Kwamiti da ke ba da shawara a kan *Penal Code*, ya tabbatarwa waxanda ba Musulmi ba da cewa *Penal Code* ba zai kawo cikas ko taqaddama da shari'an al'adu da gargajiya ba. Daga qarshe, Wazirin Sakkwato, ya ce, *"na miqa godiyarta ga duk waxanda suke aikin shari'a a wannan Jihar a Koton Alqalai xari biyu da sittin (260), da kuma Kotun Gargajiya xari huxu da casa'in da huxu (494), tare da Kotun Majistare, da Babbar Kotu. Waxannan kotuna na sauraren*

xaruruwan qararraki a kowace shekara, amma ba a cika jin xuriyarsu ba. Wannan ya nuna adalci da rashin nuna bambancin waxannan Kotuna, wajen tafiyar da ayyukansu. Yawancin ma'aikatan Kotunan ba su sami damar ganin wannan kyakkyawan gini ba, saboda haka waxanda suka samu wannan damar a wannan rana, to, su tuna fa aikinsu ba mara amfani ba ne. Saboda ayyukan Babbar Kotu da Kotun shari'a ta Xaukaka qara sun kai qololuwa ne bisa kafaxun kyakkyawan aiki da tsari tabbatacce da qananan kotuna ke bi."

Wannan mashahurin Malami na gama jawabinsa sai, Mai girma Firimiya ya miqe don ya gabatar da na sa. A cikin jawabinsa, Sir Ahmadu Bello ya ce "Buxe wannan Babbar Sabuwar Kotu, yana da muhimmanci babba ga Arewa." Saboda a watan Maris ne Jihar ta samu gabatar da tsarin *Penal Code*. Firimiya, ya ce: "Wannan ya nuna wa duniya qudirar aniyarmu ta sanya tsarkakakkiyar alqibla a tsarin mulki da kuma gyaran tsarin shari'a waxanda dukkansu suna nuna alamar tsayuwa tsayin daka da mu ke yi da kuma gyaran tsarin Jiha da a ke yi." Daga nan sai Firimiya ya ce yana alfahari da shugabancin gwamnatin da ke waxannan gyare-gyaren, ya kuma yi gargaxi da kada a sassauta wajen aiwatar da waxannan gyare-gyaren.

Don kowace hukumar kotu ta fahimci sabon tsarin *Penal Code*, sai Firimiya ya ce: "Ana koyar da wasu darussa ga shugabannnin kotun Alqalai da kotun Gargajiya a Makarantar koyon aikin mulki ta Zariya. Firimiya ya qara da cewa, gwamnati ta lura da aiwatar da ayarin tsarin shari'a, abu ne mai muhimmanci sosai wanda ke gabanta a yanzu. Daga qarshe, Sardauna ya taya Ministan Ayyuka da ma'aikatansa murna, ya kuma yi fatan nasara ga hukumar shari'a da kuma fatan zata ci gaba da yin adalci ga kowa ba tare da nuna son kai ko tsoro ba.

Sir Gawain Bell ne ya yi jawabi daga qarshe, inda ya nuna farin cikinsa a ganin wannan qasaitaccen gini wanda kuma ya qarawa wannan hedkwatar ta jiha qawa da babban matsayi, wanda bai tsaya a Arewa ba, har da duniya baki xaya. Saboda a yanzu duk hankalin duniya ya juyo ga Nijeriya ne domin kusowanta da samun 'yanci.

gwamnan ya ce Ko da yake ba a riga an fara aiki da *Penal Code* ba amma an riga an zatar da shi qarqashin doka. Ya qara da cewa yana nuna sha'awarsa ga dokokin shari'ar musulunci saboda; "kyau da jurewar dokar shari'ar musulunci da kuma muhimmancinta a wannan jiha zai havaka idan aka naxa Alqalin Alqalai wato "Grand Kadi." Daga qarshe ya ce: "Xazu-xazu ne muka shiga wannan gini ta qofofinsa, wanda yake tushe kuma alamar adalci. A yanzu ne kuma muke shiga wata qofar sabon falle. Ubangiji ya baiwa wannan babbar Kotu wadda aka gina da harsashi qarfafa adalci don ta jurewa zamani mai zuwa, da kuma a waxannan

shekaru doka da waxanda suke ba da ita su zama masu daraja da aminci a idon mutane."[1]

Hamdala Hotel

Garin Kaduna a matsayinsa na hedkwatar Arewa ba shi da Otal babba da ya dace da zamani. To, bayan shekara xaya da samun 'yanci sai aka samu labari mai farantawa daga gwamnatin Firimiya. Za a gina Otel na fam 750,000 a Kaduna Firimiya Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello zai aza harsashin ginin sabon Hotel a Kaduna a ran Laraba, 4 ga Janairun shekarar 1961. Wannan Hotel da kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa zai gina an qiyasta za a kashe fam dubu xari bakwai da hamsin (£750,000) wajen gininsa. Kuma bayan shekara biyu za a qare ginin. Kamfanin yana shirya yadda za a kira wannan Otel na Kaduna. Daga bisani an sa masa suna"Hamdala Hotel" Otel xin, idan aka gama zai iya xaukar baqi maitan da goma (210), kuma zai zama irin na zamani ne. Za a sami xakuna casa'in na mutane xaixai da kuma xakuna hamsin na mutane bibbiyu. Akwai waxansu xakuna goma don amfanin manyan baqi.

Abubuwan jin xadi da za a sama wannan Otel sun haxa da wurin rawa da zai xauki mutane xari biyar, da wurin cin abinci na jama'a da zai xauki mutane maitan da hamsin, da wurin cin abinci na mutanen da ke zaune a wurin da zai xauki mutane metan. Har'ilayau akwai xakin sinima na rediyo mai hoto da zai iya xaukar mutane metan da hamsin zuwa xari uku. Za a sami wurin wanka da ya yi dai-dai da wanda za a riqa gasar ninqayi da shi, da kuma lambu wajen shan iska mai qayatarwa. Duka gine-gine za a sanya masu injin na dai-daita iska mai daxi, wato *Air Condition*.

Abubuwan jin daxi ba su tsayanan ba. Kowane xaki na barci za a sanya masa telifon, rediyo da rediyo mai hoto na zamani. Za a sami gidan waya, da wurin aski da yin kitso na maza da mata. Wato dai Otal xin zai yi dai-dai da kowane Otal na duniya. Wannan Otal wanda zai kasance mai hawa goma sha-biyu ne, zatinsa zai kai qafa xari da hamsin. Ba shakka wannan Otal zai jawo baqi daga kowane sashe na duniya. Ba a raxawa sabon Otal suna ba, amma ana fata a ba da wata sanarwa nan gaba.[2]

Wannan Otal ne irin na zamani waxanda aka qayatar da su da kayan alatu da na'urar sanyaya xaki. A lokacin da yake aza tubalin gina wannan makeken otal a cikin watan Janairun shekarar 1961, Firimiya, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato ya ce: "Wannan otal zai cika wata buqata mahimiyya. Ana kuma sa ran zai ci gaba da samun qarin kwararowar manyan baqi daga sassan duniya masu nema da kuma bayar da shawarwari akan taimako da abokantaka."

---

1 *Nigerian Citizen*, No 782, Asabar, 7th November, 1959

2 GTK 16 Disamba, 1960

Don qayatar da garin Kaduna da kuma mazauna cikinta su samu wajen nishaxi irin na zamani da kuma samun wajen saukar baqi, sun sanya Gamji gina wannan shahararren otal. An gina wannan otal gidan sama mai hawa shida, akwai xakuna iri-iri cike da kayayyakin alatu irin na zamani guda saba'in da takwas.

Wannan otal na da isasshen wajen ninqaya. Akwai wajen kiwon dabbobi iri-iri kamar su jimuna da birai da dai sauran halittun Ubangiji masu ban sha'awa, waxanda sun taimaka wajen qayatar da wannan Otal.

Buxe Tashar Mota

A matsayin Kaduna Hedkwatar Arewa sai ta kasance babbar mahaxar tafiye-tafiye daga sassa dabamban na Arewa da qasa baki xaya. Don a qara havaka matsayin Kaduna Jamsin sai aka gina wa garin babban tashar mota, wanda aka yi bikin buxewa. Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Ahmadu Sardaunan Sakkwato ya buxe sabuwar tashar motar Kaduna wadda aka kashe jaka arba'in a wajen gina ta. Mutane jingim suka taru don kallon shagalin buxewa.

Lokacin da Firimiya ya iso wajen wannan shagalin biki sai muqaddashin Kantoman Kaduna, Mr R. N. Barlow Poole da mataimakinsa malam Muhammadu Sambo suka tarye shi. Daga nan Kantoman ya miqa masa almakashi ya yanke wani zare da aka gitta a qofar shiga tashar motar, ya je ya zauna a kujerarsa. Cikin maganar da Firimiya ya yi ya ambaci maganar buxe kadarkon Kaduna da ya buxe da sauran abubuwan da gwamnati ta yi a Kaduna tun lokacin da aka kafa ta, ta zama Hedkwatar Jihar Arewa.

Sardauna ya ce ya yi farin ciki da buxe sabuwar tashar mota. Ya godewa Kantoma da ma'aikatansa da dukkan waxanda suka yi ginin tashar motar. Ya qarasa da cewa, "Na tabbbata za a samu buqatar kashe kuxi da yawa in dai za mu gina Hedkwatan da ta cancanta ga Jiharmu. Amma komai yawan kuxin da muka kashe, Kaduna ba za ta ci gaba ba sai mutanenta sun ci gaba,sa'an nan kowane xaya da ga cikinku na iya taimakon ci gaban hedkwatar kan tsanaki. Da za a buxe tashar motar ya ce, "Allah Ubangiji ya kawo zaman lafiya da arziqi gare ku duka."

Yana buxe tashar sai aka zaga da Firimiya a wannan sabuwar tasha wadda ta na da faxi, don har akwai sito da runfunan saida abinci da wuraren saida mai. An karkasa tashar kashi-kashi ne don ya taimakawa fasinjoji su sami motar da suke buqata cikin lokaci. Motocin da za su Zariya, Gusau da Sakkwato an sanya su a kashi na farko, na kuma Zariya, da Katsina, da Kano, da Maiduguri a kashi na biyu. Jos da Bauci, da Makurxi, da Enugu a kashi na uku. Kwantagora, da Bida, da Ilori da Ibadan da Ikko a kashi na huxu. Motocin taksi su na qarshen Yamma da tashar.

Ita wannan tasha ta taimaka sosai wajen samun motocin tafiya zuwa garuruwa da daban-daban, kuma ta taimaka wajen sauqaqewa fasinjoji masu zuwa wannan hedkwata. A matsayin Kaduna na farfajiyar Arewa tana samun qaruwar zirga zirgar jama'a daga kowane sashe na Nijeriya. A kuma harkar kasuwanci sai

wannan gari ya qara bunqasa saboda qaruwar kamfanoni waxanda suka tilasta samar da bankuna.

Hada-hadar kasuwanci ba za ta inganta ba sai da tallafawar bankuna. A matsayin Kaduna na farfafiyar Arewa, bunqasa bankuna yana xaya daga cikin ayyukan da Sardauna ya yiwa wannan gari.

Buxe Sabon Banki

Manyan mutane sun hallara a wajen bikin buxe sabon ginin banki a Kaduna. A gaban Lord Harlech, Sarakuna, da kuma sauran manyan mutane, Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Ahmadu ya buxe sabon bankin Afrika ta Yamma a Kaduna ran talata. Takanas shugaban bankin, Lord Harlech ya zo daga Ingila saboda shagalin buxe wannan banki.

Cikin jawabin da Firimiya ya yi, ya ce an girmamashi qwarai da aka ce ya buxe wannan sabon gini a Kaduna.Ya ce ko da yake ginin sabo ne,amma duk da an sani tuni bankin nan ke da reshe a Kaduna,yau shekara arba'in ke nan. Sardauna ya ce abubuwa da ke faruwa a zukatansa, wata ilimi ce ta ci gaba, sa'an nan yana fata a ci gaba da amincewa da darektocin wannan bankin,game da sha'anin ciniki da sana'o'i na Jihar nan gaba xaya da kuma hedkwatan nan.

Firimiya ya ce abin farin ciki ne a ji cewa daga cikin rassan bankin nan sittin da takwas (68) da ke Afirka, goma sha-huxu (14) suna Jihar Arewa ne. Idan Jihar nan ta ci gaba,muna fata bankin za ta kafa rasussunanta a wuraren da ba su da banki. Na sani ra'yin bankin nan ta xauki mutanen qasar nan aiki a rassanta, amma waxanda za a xaukar nan,wajibi ne su zamasu na da ilimi na sekondare. Ya ce:

> *Na yi baqin ciki da jin cewa 'yan Arewa kaxan ne suka cancanta, suka aika wa bankin, takardun neman aiki.Ina fata samari 'yan Arewa lokacin da su ke tunanin abin da za su yi, kada su mance da damar da wannan banki ya bayar ko sauran bankuna.*

Firimiya yaci gaba da cewa abin faranta rai ne a ji cewa masu riba cikin bankin kuxin su ya kai fam miliyan xaya da rabi. Waxannan sun tanadi jari ke nan na raya aikace-aikacen bankin a qasashen Afirka ta Yamma.Ya ce yana fata kashi da dama na wannan jari za a yi amfani da su sosai a Jihar nan,wadda take ta raya sha'anin sana'o'inta.

Sir Ahmadu Bello ya faxi muhimmancin zuba jarin qasar waje ga qasar nan ya ce, "Muddin ana son qaruwar arziqimmu ya qaru ga yadda muke so, to, shekaru da dama masu tafe, za mu buqaci jari daga qasashen waje da kuma gwanayen ma'aikata da ake buqata. Mun yarda cewa mai yiwuwa ne qasashen waje xin nan su sanya jarin su a Jihar nan, sai dai ko an tabbabtar musu cewa, za a yi maraba da jarin nan da gwanayen ma'aikata na waje. In haka ne wajibi ne ga gwamnatin jiha

ta bi da wannan tabbatarwa, mun kuwa yi." Daga qarshen jawabinsa dai ya buxe bankin nan.

Buxe Sabon Ginin Garejin Kamfani

Alhaji Ahmadu, Sardaunan Sakkwaton, Firimiyan Jihar Arewa, shi ya buxe wani sabon garejin motoci da Kamfanin UAC suka gina a Kaduna. Ran 19 ga Janairun shekarar 1957 aka yi wannan shagali, jama'a jingin sun je kallo. Cikin jawabin da ya yi, Sardauna ya ce:

"Janar-manaja, Ministoci, Jama'a maza da mata, in a matukar farin cikin halartar wannan biki, na buxe sabon garejin UAC a Kaduna.

Akwai kuwa hujjoji biyu da suka sani murna. Ta farko, kullum muna murnar ganin an kafa wata sabuwar harakar ciniki a babban birnimmu. Ina sa rai qwarai nan gaba sha'anin cinniki zai havaka a Kaduna. Ita ta zama cibiyar cinikin Arewa. Na amince ainun, Kaduna ce, xakin nuna samfurin kayan sayarwa, waxanda su ke su ne masu gunad da ayyukan qasashensu, su masu kan Kaduna domin taron majalisar su. A nan Kaduna ne shugabannin ma'aikatan gwamnatin jihata kanyi shawarwari irin kayayyakin ayyuka da za ta saya, domin, ayyukan kyautata jihar.

Wannan sabon gini, tare da xaya shashen da ke qetaren hanya, da sabon Kingsway stores, da sabon Gidan Niger a Prince Edward Way, sun nuna a fili kantin kamfani masun yarda da maganan nan tawa, cewa ciniki zai havaka ne a Kaduna.

Hujjata ta biyu, ita ce a bisa alama ni kaina ta shafa Misalin shekara biyu da suka wuce, na sha jin qararraki daga jama'ar da ke ziyartar Kaduna, cewa ba su iya samun waxansu abubuwan motocinsu. Na ambaci waxannan qararraki ga shugabannin Kantin Kamfani a London, abin mamaki-amma fa mamaki mai daxi ba jimawa suka shaida mini, cewa kayayyakin motoci dai sun smau, sa'an nan za su gina gareji a Kaduna. Wannan kam ya wuce abin da na sa rai za a samu, don haka na gode wa wannan gama kai da UAC ta nuna cikin wannan sha'ani. Na amince irin wannan gama kai tsakanin gwamnatin Jiha da kamfunan ciniki zai inganta, ya bazo ko'ina cikin Jihar nan.

Kafin in gama maganata, ina so in ambata Kantin Kamfani fa ya buxe wata makaranta, Technical Training School, a Kano domin koya wa yaran Arewa sana'o'i. Ina fata matuqa wannan kyakkyawan nufi zai jawo hankalin 'yan Arewa da yawa, su shiga makarantar nan." Daga nan ya buxe garejin.[1]

A shirin gwamnatin Sardauna shi ne taga kowane xan Arewa yana da aikin yi wanda ya dace da iliminsa da qwazonsa. Ko kaxan gwamnati cewadda ba ta son

[1] GTK. 25 – 1.57

zaman banza ko zaman kashe wando. Firimiya na so ya gina Arewa ne a kan Aiki da Ibada wata aqida da ta dace da addini da al'adun mutanen Arewa. Da sana'a akan san Arewa, ta yi kumafice a harkar addini. Domin haka ne ma ya yi bovvasa wajen cusawa 'yan Arewa wata muhimmiyar aqida wadda ta dace da kowane zamani wato aqidar Aiki da Ibadah.

KASHI NA GOMA SHA-XAYA

AIKI DA IBADA

Mr. C. Graham, Sufeton Ilimi, ya yi tsokaci da cewa:"Akasarin mutane da ke wajen lardunan Arewa sun xauki Bahaushe xan tireda ne wanda ke da yawan talla a qauyuka da garuruwan Arewa, inda yake zuwa sana'ar koli a waxannan garuruwa. Bahaushe ya yi suna wajen sufuri da kasuwanci domin kuwa Hausawa sun watsu a duk lungunan Nijeriya, da duk faxin Arewacin Afirka har ya zuwa Gabas Ta Tsakiya da Saudi Arabiya, da Arewacin Qudus wato Jerusalem."[1]

Ko shakka babu, Hausawa sun yi suna sun kuma shahara wajen sufuri da kasuwanci a duniya baki xaya. Domin haka ne masuka watsu a Nahiyar Afirka, da Asiya da Turai.

'Yan Arewa an san su da sana'a da son addini. Sana'o'i a cikin rayuwar 'yan Arewa suna da yawa, da kuma matuqar muhimmanci. 'Yan Arewa sun yi suna a sana'o'i masu yawa, musamman a sana'ar noma wadda ita ce babbar sana'a. Akwai kuma sana'o'in hannu, waxanda ake sarrafa wani abu domin a samar da wani abu. Alal misali, akwai sana'ar qira, inda maqera ke sarrafa qarfe don su samar da kayan noma kamar su garma, da fartanya, da magirbi, da wuqaqe, masu da takubba, da adduna, da basilla da makamantansu. Qasar Arewa ta yi suna wajen qera makamai kamar su kibiya da takobi da garkuwa da sauransu. Maqeran wannan zamani sun yi suna, wajen nuna hikima da basira a wajen qera kayayyaki iri-iri da suka shafi rayuwar bil-Adama. A kusan kowanne birni akan samu Unguwar Maqera da Sarkin qira.

Idan ka xebe noma da qira, babu sana'ar da ta fi saqa taimako ga mutum. Arewa ta yi suna a wannan sana'a shekaru aru-aru kafin zuwan Turawa. Ko da suka shigo wannan qasa, sun yi mamaki da suka tarar jama'a na sarrafa auduga wajen yin saqe-sake iri-iri. A da can, kafin xan-Adam ya san saqa, ba shi da wata sutura, sai ta xaura ganye ko vawon ita ce. A inda aka ci gaba ne ake xaura fatu. A wasu al'ummomi kuwa, tsirara mutane ke yawo. An kuma samu shekaru da yawa, xan-Adam na ganin auduga tana tsira cikin daji, amma bai san abin da zai yi da ita ba. Saqa tana nuna ci gaban da al'umma ta yi saboda haka ne Turawa suke mamakin ci gaban da 'yan Arewa suka yi a fannonin rayuwar xan-Adam, a lokacin da suka shigo Arewa, a farkon shekarar 1903. Domin kuwa al'ummomi masu yawa a wannan qasa da qetare ba su kai ga wannan daraja ba.

---

[1] *The Nigeria Year Book* (1937), vol. 2. NOS 11-20, shafi na 19

Turawa sun tarar da 'yan Arewa da auduga, mata kuma suna kaxi ana saqa. Akwai saqa iri biyu, ta maza da ta mata. Ta maza ita ce ta fari da saqi. Ta mata kuwa, ita ce ta gwado. Kayan saqa na maza sun fi na mata yawa. Na mata su ne shika-shikai na ita ce, da xan-jifa, da allera, da akwasa. Amma na maza, bayan allera, akwai qoshiya, da matsefi, da kunkuru, har da su kai-ka-zo. Saqar maza galibi sana'a ce ta gado, a birane ma har unguwa gare su musamman.[1]

Saqa ta mata ta kowa ce, maganin zaman kawai a gida. Don haka akwai masaqa a kowane gida inda in ba a saqar gwado, to, ana saqar hula. Saboda haka kowane gida na da sana'ar yi, abin da ya taimaka gaya wajen bunqasa tattalin arziqin qasar Hausa. Domin daga gidaje a ke saqa gwado, da majayi, da saqi da zane da sauransu, ake kaiwa kasuwa.[2]

A sana'ar dukanci kuma, akwai dukawa masu sarrafa fata suna yin jakunkuna, da takalma, da kayan dawaki, da layu, da guraye da karbuna, da kube, da xamaru, da alabe da bazar yan dambe, da walki da sauransu. Sai kuma sana'oi na yin amfani da jari, da qwarewa kamar kasuwanci da gini da tallau.

Aiki da Ibada da sana'a suna daga cikin abubuwan da Sarakuna suka baiwa muhimmanci sosai. A duk faxin qasar Hausa, yara na tashi ne da Tarbiyya, da ilimin addini da sana'a. Saboda kafin yaro ya balaga ya kai munzilin mutum mai hankali, ya fahimci addininsa da kyau, ya kuma sami horo wajen sana'ar gidansu ko unguwarsu ko kuma wata sana'a da ya zava ko aka zava masa. Saboda haka ne ma mutum mai sana'a yake da muhimmanci da kima a idon jama'a da hukuma. Kowane mai sana'a, nema yake ya shahara a wajen sana'arsa. Don haka ne duk wanda ya yi fice a sana'arsa, sai Sarki ya karrama shi da sarautar da ta dace da shi. Don haka ne ake samun Sarakunan sana'o'i daban-daban kamar Sarkin Qira da Sarkin Magina, da Sarkin Noma, da Sarkin Kasuwa da sauransu.

Saboda muhimmancin da hukuma ta baiwa sana'a a rayuwar mutum, ya sa aka samu unguwanni da suka yi fice a sana'arsu, suka kuma taimaka gaya wajen ci gaban al'ummarsu. Wannan ya sa ake samun unguwanni kamar; Unguwar Magina da Unguwar Maqera, da Unguwar Marina da sauransu. A duk waxannan unguwanni akwai Sarakuna da ke kula da sana'o'i bisa tsari da kuma neman hanyoyin da za su bunqasa sana'o'in da samar masu kasuwanni birni da qauye. Saboda irin wannan tsari da ya yi shekaru aru-aru da kafuwa ya baiwa jama'a kyakkyawan horo, wajen yin aiki nagari da riqe aiki ko sana'ar da mutum ya sani sosai. Alal misali, Marina ba su watsar da sana'ar rini su koma sana'ar qira saboda ganin aikin qira ya fi kawo riba. Haka kuma waxannan Sarakunan sana'o'i iri-iri,

---

[1] Ibrahim Yaro Yahaya da Abdulqadir Xangambo, *Jagoran Nazarin Hausa*, Northern Nigerian Pub. Comshafi na Ltd., (1989) Zaria, shafi na 173

[2] *Ibid*. shafi na . 173-174

ba su shiga aikin mulkin da ya shafi ikon mai unguwa ko dagaci ko hakimi. Saboda ikon sarautarsu ta tsaya ne akan shugabancin masu irin sana'arsu.

A wajen fannin ilimi kuwa akwai Unguwar Malamai da Unguwar Alqalai waxanda suke da babban matsayi a biranen Arewa. Duk abubuwan da suka shafi malamta da alqalanci, Sarki kan tuntuvi masana a waxannan unguwanni ta Alqalai da Malaman fadarsa.

Hatta makaxa da mawaqa na da unguwarsu domin su masuna ba da tasu gudunmawa wajen ci gaban al'umma. Wani abin sha'awa kuma shi ne makaxa da mawaqan wancan zamani sun rabu kashi-kashi. Akwai mawaqan Sarki da sarauta, akwai mawaqa da maqixan noma, akwai mawaqan dambe da kokawa da sauransu. Kowane mawaki ko maqixi, qoqari yake ya nuna bajintarsa, ya yi kuma suna a fagen qixa ko waqarsa. Dalilin haka ya sa suke da karsashi da hikima a wannan sana'a tasu.

A cikin wannan tsari ma, akwai unguwar Miskinai kamar makafi da kutare da guragu. Akwai su da Sarki wanda zai kula da su ya kuma kai kukansu ga hukuma, idan buqatar haka ta taso. Waxannan naqasassun ba ana qyamarsu ba ne, amma an ba su unguwarsu ne saboda kyakkyawan tsarin da ke akwai a biranen Arewa, wanda ya baiwa duk mai sana'a kafa unguwarsa ta musamma. A wancan lokaci kuwa Naqassasu ke bara, haqqin hukuma ne ta kula da su, kamar yadda hukuma ke kula da kowace unguwa da sana'arta.

A irin wannan tsari na kafa unguwanni na sana'o'i, kusan a ce babu kamarsa a Afirka a wannan zamani. Shiri ne da ke son gwani wato "expert" da kuma nuna gwaninta ko "expertise." Duk kuma wanda ya fito da gwanintarsa har ya yi fice, sai Sarki ya karrama shi da muqami ko muhimmiya wadda za ta yi masa qaimi ya kuma qara himma ya kuma zama abin misali a al'ummarsa. Arewa ba al'umma ce da ba ta son gwani ba wato *anti-hero society*. Al'umma ce da ta san cancanta wato "worth" da inganci wato "value." Rashin son gwani wata halayyace da ta hudo kai daga qarshen Siyarsa Farko. Wannan al'adar ta taimaka gaya wajen maida Arewa kidahuma. Idan aka lura da wannan tsari za a ga cewa duk waxanda suka zo Kaduna, sun taho da wata sana'a da su ka iya. Amma saboda gari ne na ma'aikatan gwamnati ba a kafa unguwanni a bisa sana'o'i ba.

A lokacin da Turawa suka zo Arewa, sun tarar da Hausa – Fulani da Barebari da Nufawa da Yarbawa da sauran qabilu nada sana'oi iri-iri. Ana iya taqaita waxannan sana'oi da jadawali kamar haka:[1]

---

[1] Ibrahim Yaro Yahaya da Abdulqadir Xangambo, *Jagoran Nazarin Hausa*, Northern Nigerian Pub. Com. Ltd., (1989) Zaria, shafi na 166



Qasar Hausa ta yi kuma suna a wajen malanta wato koyar da ilimin addini. Akwai kuma makaxa da mawaqa waxanda suka yi suna wajen nuna hikima, da basira a sana'arsu. A wannan lokaci Sarakuna sun sanya ido sosai wajen hana zaman banza ko zaman kashe wanda. Don haka kowane mutum ka samu tallau ne, ko aikatau in ba haka ba, sai a tura shi wajen aikin gayya wato *Communal Work* ko aikin tilas wato *Forced Labour*. Abin da Sarakuna suke son gani shi ne kowanne mutum ya sami sana'ar yi, yana kuma yinta bil haqki da gaskiya babu xungushe ko almundahana. Kwaram! Sai ga guguwar Mulkin Mallaka za ta tafi da sana'a daga zukatan 'yan Arewa.

A wajen Addini kuwa, kowa ya san Arewa wajen suna da suka yi wajen ba da gudunmawar ci gaban addini musulunci da addinin Kirista ba a Afirka ba, a duniya baki xaya. A harkar Addinin musulunci kuwa, kowa ya san gudunmawar da Daular Barno da Daular Usumaniya suka bayar ga nahiyar Afirka da duniya baki xaya. Saboda haka ne Sardauna ya lura idan aka samu 'yan Arewa suke riqe waxannan abubuwa guda biyu: *Aiki da Ibada* to, babu shakka za su shahara a duniya baki xaya. Da wannan kyakkyawar niyya ce, Firimiya ya xauki wannan gwagwarmayar yaxa aqidar Aiki da Ibada, ya kuma dage sosai don wannan shiri yaci nasara.

An kafa harsashin Arewa akan waxannan abubuwa guda biyu: Aiki da Ibada. Aiki wanda ya qunshi sana'o'i iri-iri yana xaya daga cikin shika-shikan siyasa ko

mulki. A qa'ida ta shida Muhammadu Bello, a littafinsa *Usulussiyasati*, ya ce: "Wajibi ne ga shugaba ko kuwa Sarki ko Gwamna ya yi qoqarin tanadi da aiwatar da ayyukan duniya da na lahira ga jama'arsa. Haka kuma ya zama tilas gare shi da ya yi aiki tuquru ya kuwa mayar da himmarsa ga sana'o'in hannu ya kuma qarfafa gwiwar masu sana'o'i; kamar su manoma da maxunka da kuma marina..." [1]

Idan aka ce 'Aiki', to, kowa ya san abin da ake nufi. Amma idan aka ce 'Ibada' sai a xauka ana nufin ibadar musulunci kawai. A dalilin haka Sir Ahmadu Bello ya fayyacewannan kalma da nufin Ibada ga dukkan mabiyin addinin da ya zavawa kansa, ko addinin Musulunci ko na Kirista. Ya kuma zama mai yin kira ga mabiyan waxannan addinai da su sadaukar da kansu wajen Aiki da Ibada.

Firimiya ya gayawa Majalisar Mishan ta Mazhabin *Protestant* cewa iqirarin jinjirar Jihar Arewa shi ne "Aiki da Ibada." Wannan shi ne Taken Arewa na musamman lokacin da ta samu Mulkin kai, a shekarar 1959. Musamman Firimiya ya je Jos don ya yiwa Majalisar Mishan xin nan jawabi. Bishop na Jihar Arewa, Rt. Rev. F.E.L Mort shi ya raka shi.

A farkon jawabin Firimiya sai da ya bayyana irin ci gaban mulki a Arewa da irin canje canjen da za su auku nan gaba. Ya kuma tavo magananar mulkin kan da Nijeriya gaba xaya za ta samu a ran 1 ga Oktoban shekarar 1960.

Game da maganar ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, ya ce ana matsawa sosai wajen tafiyar da manufar, misali ma yanzu akwai kusan 'yan Arewa arba'in da ke muqamin Di'o, kowane lardi yana da Di'o 'yan Arewa xaya ko biyu za kuma a sami da dama nan gaba. Wajen ci gaban nan da aka yi, ya ce yana godewa aikin da Mishan suka yi. Ya ce yana farin ciki da ya fahimci, cewa akwai zumunci da haxa kai tsakanin gwamnati da Mishan. "Ba za mu yi musun bambancin da ake samu a kai a kai ba, amma na amincewaxannan bambanci idan suka faru, ana iya daidaitawa kansu cikin hankali kwance. Ya ce, "Banbancin addininmu bai kamata ya hana mu ci gaba da aiki tare don amfanin mutanenmu ba."

Firimiya ya gaya musu qungiyar da aka aika, wadda ta tara Musulmi da sta zuwa Turabulus, Pakistan da Sudan – duka sabbin qasashen da ke mulkin kansu, kuma yawancinsu Musulmi ne – don su ga yadda Gwamnatocinsu ke tafiyar da harkokin mutanen da qabilarsu da addininsu ya sha bamban. "Abin da muka qaru daga waxxannan qasashe yana da bam sha'awa da amfani. Saboda haka muna duba hanya mafi kyau da za mu sanya aiki da abin da muka karu."

A kan 'yancin addini kuma Firimiya ya ce, "gwamnatimmu, gwamnatin 'yan Arewa ce, Musulmi da Kirista, waxanda su ke son bin koyin addininsa yadda ransu ya yi masu daxi. Ina so in qara tabbatar muku cewa, jawabin da na yi a madadin gwamnati a bara yana nan yadda yake, sa'an nan abin da mu ke nufi, muna nufinsa ne har cikin zuciyarmu."

---

[1] Mujallar Hukumar Tarihi Ta Jihar Sakkwato, shafi na 96

A game da haqqin 'yan-Adam, kuma ya ce lokacin da aka yi Taron London an yi shawarwari daki-daki kan yadda za a rubuta haqqin 'yan-Adam cikin shirin Mulki ya ce za su yarda da shi, cewa wurin da ya shafi 'yancin addini, am bayyana shi cikakke sosai.

Sardauna ya yi Kira ga Samari

A kan wannan kyakkyawan harsashi na Aiki da Ibada ne, Sardauna ya xora gininsa. Idan akwai abu guda bayan ilimin da Firimiya ya so ya cunkusa wa 'yan Arewa a zukatansu, to, babu kamar Aiki da Ibada, wadda don muhimmancinsa ya zama taken Arewa baki xaya. Sardauna bai yi qauren baki ba a bikin shekara xaya da tunawa da ranar samun Mulkin Kai, na ranar 15 ga Maris xin shekarar 1960. A wannan rana ce ya qara jaddada aniyarsa ta ganin wannan tsohuwar aqida ta qarbu ga 'yan Arewa, a wannan sabon zamani. Ga kaxan daga jawabinsa a wannan rana:

"Ina son in yaba maku kamar yadda na yi bara, taken Jiharmu, shi ne"Aiki da Ibada." Ba wurin lalaci, nuna ragwanci da sakarci ko zaman banza a wannan Jiha. Duk da tsofaffin xabi'u da al'adunmu na gargajiya, muna fa cikin wannan sabuwar duniya a kuma qaramar qasa saboda haka im ba bu aiki tuquru tare da sadaukar da kai, ba za mu cimma burin tadda qasashen da suke gaba da mu ba, wajen kula da lafiya, da raya qasa da jin daxin jama'a. Amma aiki tuquru tsagwaransa zai ba da riba kaxan sai fa mun haxa da Ibada tare da imani, da gaskiya, da adalci."[1]

A duniya yanzu a kwai qasashen da suka yi watsi da addini da sunan ci gaba, suka kuma duqufa wajen aiki, amma ribar da suke samu kaxance, saboda ci gaban su, ci gaban mai haqar rijiya ne. Ba ci gaba tabbatacce sai wanda jama'ar suka haxa Aiki da Ibada. A lokacin wannan biki, Sardauna ya qara kira da babbar murya ga Samarin Arewa.

A sabili da haka ba wanda zai yi mamaki, ganin Sardauna ya himmatu wajen qarfafa 'yan Arewa akan sana'a. Domin wataqila ya hango sabon salon Mulkin Mallaka zai tafi ya bar mu babu sana'a sai bara da tumasanci. Sardauna ya riqe muqamin Ministan En'e da Raya Qasa da jin Daxin Jama'a, ya himmatu, ya kuma ware-dantse don ya cimma nasarar manufofin wannan muqami nasa. Haqansa kuma ya tadda ruwa. Ya gina ma'aikatu, da masana'antu, da kamfanoni masu yawa waxanda za su baiwa 'yan Arewa aiki iri-iri. Domin haka sai ya riqa ziyarsu a lokaci lokaci, saboda aiwutar kara sai da izawa. Alal misali, Firimiyan Jihar Arewa ya ziyarci wajen aikin kayan shaye shayen wanda yake ana cikin aikinsa, a watan Maris na shekarar 1962 wanda ake sa ran za a kashe kuxi kamar fam

[1] Stephen A. Amune, *Work and Worship*, shafi na 35

miliyan xaya. A wurin ne kuma Manajan ciniki na kamfanin, Mr. J.A.C. Osborne, ya shaida wa Firimiya, cewa wannan wuri idan aka qare shi zai ba 'yan Nijeriya kamar xari huxu aikin yi.

Firimiya ya ziyarci Masaqar Kaduna inda aka faxa masa cewa wurin yin saqa na sashen wurin, wanda yake ba da daxewa ba zai riqa ba da yadi dubu xari uku (300,000) na tufafi a cikin mako xaya. Saboda haka sai Sardauna ya ce idan aka fara yi kuwa zai yi riga da qyallen farko da aka saqa, ya zama tamkar wani abin nuni na Saqar Jihar Arewa na farko da aka yi da audugarta.

Sa'adda ya isa wani kamfani da ake kira Thomas Wyatt & Sons, wato wurin adana littattafai da kuma gyaran abubuwan amfani na ofis, wanda yake kamfanin ya fara aiki a cikin watan Agusta ne, Sir Ahmadu ya ga 'yan mata Arewa suna yin aiki, kuma wani ma'aikacin wurin ya shaida masa, cewa yanzu ne kamfanin ya fara yaqin neman ci gaban sayarwa ba da jimawa ba.

Sardauna ya yi farin ciki da ganin ci gaban sana'o'i a cikin Jihar Arewa wanda ya bayyana tafiyar sana'a da cewa, "A hankali a ke tafiya amma tabbtacciya, tana da daraja." A wannan ziyara ya tafi tare da Ministan Ciniki da Sana'o'i na Jihar Arewa, Mr. Michael A. Buba, da Ministan Tsara Arziqin Qasa, Alhaji Muhammadu Bashar, da Ministan Ilimi, Alhaji Isa Kaita, Wazirin Katsina, da Muqaddashin Shugaban Kamfanin Raya qasa na Jihar Arewa, Alhaji Muhammadu Ladan, tare da Sakatarensa Alhaji Abubakar Tunau.[1]

Jama'a sun ga abin al'ajabi lokacin da Sardauna ke dawowa daga ziyarar da ya kai tashar Talbijin da ke Jaji inda ya duba babbar na'urar tashar watsa shirye-shirye wato Transmitter Station, a watan Maris xin shekarar 1962. Saboda daga kan titi sai ya hango wani gida da aka rubuta taken Arewa: Aiki da Ibada. A dalilin haka sai ya ce a kira mai wannan gida, ya yabeshi ya kuma qara faxawa jama'a muhimmancin wannan Taken Arewa. Bayan haka sai Sardauna ya bashi kyautar fam goma (£10) wato ya bashi tallafi don ya gama ginin gidansa da ke xauke da Taken Arewa.[2]

Aqidar Aiki da Ibada tana da muhimmancin gaske a rayuwar Musulmi don kuwa Sayyadina Umar (Alaihissalam) wani lokaci ya kan yi fitar burtu ya shiga cikin jama'arsa yana bincike akan ayyukansu. Idan ya sadu da mutum ya kan tambaye shi, "shin ba ka faxa min sana'ar ka ba?" Idan Amirul-muminina bai gamsu da sana'ar wannan mutumin ba, sai ya yi masa nasihar cewar: "Dan Allah kada ka bar rayuwarka ta zama qwamamawa ga rayuwar xan uwanka." Wato wajibi ne kowane mutum ya zama mai dogara da kansa wajen ci da guminsa ba da gumin wasu ba. A dalilin haka ne musulunci ya wajibta Aiki da Ibada akan kowane mutum lafiyayye. Akan wannan tafarki ne aka gina Arewa. Saboda haka

---

[1] GTK 2 ga Maris 1962, shafi na 1

[2] NC, No 1010, Asabar 10/3/1962

ne Sarakuna a matsayinsu na Wakilan Daular Usumaniyya suka jajircewajen ganin aqidar Aiki da Ibada ta tasirantu akan jama'arsu.

Irin waxannan ziyarce-ziyarcen da Sardauna ke yi ya samo asali ne daga rangadin Sarakuna wanda yana cikin shika shikan mulki na Sarakuna ko na 'yan siyasa. Domin yaqin yaxa aqidar Aiki da Ibada ba Sardauna ne kawai yake yi ba, Sarakuna ma ba a bar su a baya ba. Sana'a na xaya daga cikin abubuwan da Sarakuna ke dubawa a lokacin rangadinsu.

Gudunmawar Sarakuna

Sarakunan Arewa ne ke zuwa rangadin garuruwa da qasashensu a lokaci-lokaci don su duba ci gaban su kuma saurari koke-koken jama'arsu, su kuma gani da idanuwansu abubuwan da suka ce ayi ko an zartar. Suna duba harkokin addini, da harkokin sana'a da kasuwanci da kuma harkar tsaro wato zaman lafiya da lumana. Sun daxe suna yaqi da zaman banza wanda ke haifar da bara da tumasanci.

Mulkin Sarakuna da zaman banza kamar wuta ne da shiva, saboda ba su haxuwa. A wannan kyakkyawan tsarin mulki, haqqin masu unguwanni da Dagatai ne da fidda duk wani kowasu vata-gari musamman masu zaman banza da gararamba a gari domin a hukunta su. Sarakuna kan tafi rangadi ne domin su ji su kuma gani yadda harkokin jama'a ke tafiya ba su dogara kaco-kan a kan labari da rahoton da suke samu ba don kuwa ai gani ya kori ji. Rangadin Sarakuna wani abu ne sananne mai muhimmancin gaske. Alal misali, a Kaduna tunda aka kafata Sarakuna ke zuwa rangadi a wannan gari. Xaya daga cikin muhimman ayyukan Sarakuna shi ne fita rangadi, inda Sarki zai sadu da Hakimai da Dagatai da jama'ar birni da qauye. A wannan lokaci zai ji koke-koken jama'arsa. Rangadin Sarakuna sai ya zama wata babbar damar ganin jama'arsu, sun himmatu bil haqqi da gaskiya wajen Aiki da Ibada.

A ranar 7 ga watan Disamban shekarar 1944 da misalin qarfe takwas na safe, Sarkin Zazzau Ja'afaru da shi da ayarinsa, ya tafi tare da kwamandan sojoji, da waxansu manyana qasarsa suka tafi Kawo. Lokacin da suka isa sun tarar da jama'a sun yi dafifi suna jiran zuwansa. Saboda a lokacin nan akwai yawan sace-sacen dukiyar jama'a da aikata laifuffuka daban-daban. Sarki ya buqaci a riqa tabbatar da sana'ar kowane mutum, domin a san nagari da kuma vata-gari. Domin duk mutumin da ba shi da wata sana'a babu shakka ba za a sa shi a cikin mutane nagari ba. Ya buqaci a riqa tsawata wa soja domin su zama abokan hurxar jama'ar gari ba abokan gaba ba. Da yake a lokacin nan jama'a sun san akwai doka, sai ya bayar da umurnin a ajiye Xan Doka guda xaya rak wanda shi kaxai ya isa ya kula da dukkan al'ummar Kawo.[1] A duk inda jama'a ke zaune, tilas a xauki matakan

[1] Abdulkarim A. G. Maqarfi, *Sarkin Zazzau: Malam Ja'afaru Dan Ishak*, shafi na 65.

tsaro don kada vata-gari su riqa aikata masha'a. Duk umarnin da Sarki ya bayar ana bi sau da qafa.

Haka kuwa aka yi xin. A nan ne Magajin Gari Sambo ya bayyana wa Sarki yawan jama'ar da ke zaune a Kawo da kuma irin matakan da ya xauka na kawar da vata-gari, waxanda ba su da sana'ar komai. Ya shaida masa cewa dukkan mutumin da aka samu ba shi da sana'a lallai ne ya tashi. Idan kuma yana da gida ne, dole ne ya sayar da gidan ya tashi domin irinsu ne varayin zaune, masu kawo haxari ga rayukan jama'a da dukiyoyinsu. Sarki ya goyi bayan wannan doka wacce babu shakka ya san za ta taimaka wajen kare al'umma shiga wani hali na rashin jin daxin rayuwa. Saboda sanin cewa a lokacin nan akwai yawan caca, da shan giya ga kuma yawan sace-sace a Kawo, sai ya umurci dukkan matan banza da su tashi kuma ya hana matan sojoji sayarwa da duk wani Musulmi giya. Ya umurci soja da kada su kuskura idan Musulmi ya je sayen giya wajensu su saida masa.[1] A tun wancan zamani, ake qoqarin ganin jama'a na bin shari'ar musulunci dai-dai gwargwado. Saboda haka ne a wannan rangadi Sarki:

Ya ce ya umurci Magajin Gari da ya tabbatar an aiwatar da wannan umurni da ya bayar; kuma ya aika masa da halin da ake ciki na bin umurnin dokar. Nan take da kansa don sanin masu sana'a da waxanda ba su da ita, ya soma tambayar mutanen da ke gaba-gaba a wajen da aka taru irin sana'ar da kowa ke yi. Nan take ya ce da jama'ar da ke wurin dukkan mutumin da ya san ba shi da wata sana'a ya tashi ya bar garin ya kama gabansa. A nan ne Babban Baturen Soja ya shaida wa Sarki cewa Unguwar Shanu ta fi Kawo lalacewa. Malam Ja'afaru ya gaya masa yana da buqatar zuwa can tun da farko, domin yana zaton haka za ta faru. Sai ya umurci Magajin Gari da ya je ya tara masa jama'ar Unguwar Shanu da na Abakwa domin yana son yin magana da su. Magajin Gari ya aikata abin da aka umurce shi da yi har ma ya yi lissafin jama'a da ke da sana'a da kuma waxanda ke zaman banza. An bayyana wa Sarki akwai matan soja guda xari biyu da biyar. A nan ya tambayi mai Unguwar Shanu matsayin zamansu a nan."Suna tare da mazansu ne, ko kuwa ya al'amarin yake?" Sai aka bayyana masa cewa waxansu matan mazansu na nan a Kaduna a barikin soja; waxansu kuwa mazansu na wajen yaqi ne, shi ne suka saya masu gida domin su zauna.

Da ya ji wannan bayani sai ya ce, 'tun da yake haka ne, waxanda mazajensu ke wajen yaqi sai su ci gaba da zamansu, domin mazajensu sun san inda suke. Waxanda kuwa mazansu ke cikin bariki su kuwa suna nan a zaune, duk sai ya umurce su da su da karuwai duka su tashi. Ya buqaci waxanda alhakkin kula da sojoji ke wuyansu da su ga lallai sun sami wata hanya da za ta hana sojoji shigowa Unguwar Shanu; ba domin komai ba, saboda gudun savani tsakaninsu da jama'ar da ke zaune a wurin. Ya yi wa jama'a gargaxi kamar yadda ya yi a Kawo;

[1] *Ibid.*

kuma ya ja kunnen mutanen da ya sami labarin idan jirgin qasa ya zo wucewa xauke da fasinja suna jifan jirgin. Ya ce duk wanda aka samu yana yin irin wannan hali za a lissafa shi a cikin rukunin mutanen da suke lalatattu, marasa aikin yi. Ya qara da gargaxin mutanen da suka mallaki gidaje da kada su kuskura su riqa ajiye mutanen da ba su da wata takamammiyar sana'a a gidajensu. Yin haka zai kawar da mutanen da ba su da burin komai a zuciyarsu ban da cutar jama'a. Wanda aka samu ya karya doka za a hukunta shi qwarai da gaske.[1]

Tafiya rangadi kan taimaka wa Sarki ganin jama'arsa da kuma jin matsalolin da ke addabar su. Saboda babu wani tsarin mulki da ya kai na Sarakuna wajen kusanta da talakawa. A duk faxin qasar Arewa zuwa rangadi abu ne da Sarakuna suka ba muhimmanci sosai. Dalili kuwa shi ne Sarakuna na nuna kishi da son talakawansu da jama'arsu baki xaya ba hanqoro suke wajen wawashe dukiyar jama'a, kamar yadda ake ta farfagandar cewa mulkinsu bai haifar da komai ba, sai zalunci tsagwaronsu. Idan wannan qagen na da qashin gaskiya da yanzu Sarakuna ba su da wata martaba a idon jama'a, fiye da shekaru arba'in da barin mulki. Hasali ma dai, kusan kowa neman wani muqami na sarauta ke yi, ba domin komai ba, sai don ya samu karvuwa ga jama'arsa.

A ziyarar da Sarkin Zazzau Jafaru ya kai Kaduna a ranar 17 ga watan Yuli, 1943, talakawan da ke zaune a Kawo sun bayyana masa matsalar da ke tattare da su wajen rashin filin da za su riqa nomawa domin ciyar da iyalansu da kuma bunqasa tattalin arziqin qasa. Filin da suke da shi ko kusa ya yi masu kaxan matuqar gaske, saboda sojoji sun gaje masu gonakinsu. A nan bai yi masu alqawarin zai duba matsalarsu nan gaba ba, domin ya share masu hawaye. Nan take ya umurce su da su shiga Afaka idan sun ga akwai wuri wanda mutanen Afaka suka rage, sai su tambayi Sarkin Afaka domin ya ba su taimakon inda za su yi noma don biyan buqatarsu. Bai tsaya da umurtarsu da yin haka ba, sai da shi kanshi ya sami Sarkin Afaka ya gaya masa buqatarsa game da kukan waxannan bayin Allah.

Shi kuma Sarkin Barnawa irin kukan da ya kai ke nan ga Malam Ja'afaru a madadin al'ummarsa. Nan da nan ya umurce su da su shiga qasar Cikun su yi noma domin akwai isassun filaye a can; kuma ya sami Sa'i ya bayyana masa. A garin Cikun kuwa Sarakunan Gwari sun buqaci da ya taimake su a mayar da makarantar boko zuwa Gwagwada. Dalilinsu na buqatar xauke wannan makaranta zuwa Gwagwada shi ne domin idan sun tafi wajen shari'a za su riqa samun damar saduwa da yaransu su riqa sanin halin da suke ciki na rayuwa da kuma karatu. A lokacin kuwa makarantar tana Gadani ne. Ya bayyana masu wannan magana gaskiya ce amma zai shawarci Baturen makaranta idan ya ga yin haka ya dace sai

[1] Abdulkarim A. G. Maqarfi, *Sarkin Zazzau: Malam Ja'afaru Dan Ishak*, shafi na 65.

a aikata abin da suke so, amma sai da kaka. Wannan ya nuna a sarari cewa bai shiga aikin wani kai tsaye ba, alhali yana da ikon yin haka.

A maimakon amfani da ikon da Allah Ya ba shi, sai ya ga ya fi dacewa da ya tuntuvi wanda alhakkin aikin ya rataya a wuyansa. Idan yin hakan, wato biyan buqatar mutanen akwai amfani, to, babu shakka za a aikata abin da suke so. Idan kuwa babu amfani bai dace da a daxaxa masu rai a cuce su ba. Aiwatar da wani abu a wurin shi ya danganta da fa'idarsa ne ga jama'ar da nauyin gudanar da mulkinsu ke hannunsa. Waxansu Gbagyi da ke qasar Kujama waxanda yaransu ke halartar makaranta a Gwagwada sun roqi Sarki da ya taimake su da a gina masu makaranta ne a Kakuri. Sun bayyana dalilinsu gare shi da cewa suna da nisa qwarai tsakaninsu da Gwagwada. A lokacin nan a gaskiya akwai matsalar kuxaxen da za a yi ayyuka irin na gine-gine.

Don haka bai yi masu alqawarin za a gina masu ba domin shi mutum ne da ya riqe gaskiya a zuciyarsa. A maimakon haka ya fito sarari ya bayyana masu cewa akwai matsalar kuxi da kuma samun malaman da za su tafiyar da makarantar da suke buqata. Ya shaida masu duk da haka zai gabatar da kukansu ga Baturen makaranta domin ya san buqatarsu; da xaukar matakin da ya cancanta domin a share masu hawaye idan har akwai halin gina makarantar kamar yadda suka buqata.[1]

Haka shi ma Sarkin Zazzau Aminu ya xau hannu, ya riqa zuwa zangadin qasarsa don tabbatar da zaman lafiya da raya qasa da jin daxin jama'arsa. A kowane rangadinsu Sarakuna na binciken harkokin sana'ar jama'a, da ilimi da addini.

A wannan lokaci, Ko da yake Sarakuna ba su da ikon mulki wanda ya kamace su, amma duk da haka Sarkin Zazzau Alhaji Shehu Idris, CFR, na zuwa taro da gwamnan Kaduna a ranar Talatar kowane mako wato *Security meeting*. A wannan taro ne ake tattauna matsolin da suke addabar jama'a waxanda kuma ake ganin sa iya tada zaune tsaye, domin a yi maganinsu. A matsayinsu na Shugabannin Majalisar Sarakuna, kowane Sarkin wuqar yanka, wakili ne na Kwamitin Tsaro a Jiharsa. Al'amarin tsaron qasa, ya fi qarfin shugabannin mulki da jami'an tsaro. Tsarin mulki irin wanda ake bi yanzu, na Gwamna da kwamishinoninsa a Jiha da shugabannin qananan hukumomi da kansiloli ba su kai wa ga jama'a kamar yadda ake so. Saboda tsari ne da ya yi bokoko a sama kamar kainuwa, jijiyoyinsa ba su tadda qasa ba. Wannan ya tilasta a sanya Sarakuna a cikin harkokin tsaron jiha da na qasa baki xaya. Saboda haka babu yadda za a shawara Sarakuna zane, a harkokin jama'a ba yau ba, har gobe. Domin mulkinsu yana da kyakkyawan tasiri a kan jama'a.

---

[1] Abdulkarim A. G. Maqarfi, *Sarkin Zazzau: Malam Ja'afaru Dan Ishak*, shafi na 62-63.

Duk da yake an qarve mulki daga Sarakuna, amma da Mulkin Soja da na Farar Hula sun kasa tabbatar da tsaro ga jama'ar da suke mulki saboda akwai gazawa a tsakanin masu mulki da jama'arsu. Saboda haka ya zama tilas a yi amfani da Sarakuna domin a yi maganin tavarvArewar tsaro, musamman a Arewacin wannan qasa. Babu yadda za a yi a samu kyakkyawan tsaro da zaman lumana a qasar da shugabanni ba sa ga maciji da jama'arsu. Haka kuma babu yadda za a samu tsaron da ake buqata, a inda zalunci ya yi katutu ga shugabanni, jama'ar kuma suka wofintar da sana'arsu, suka koma nuna qwanji, da bara da tumasanci.

Sarakuna a rangadinsu da kuma rahoton halin da jama'a ke ciki, suna ba su damar xaukar matakan maganin matsalolin da ke akwai da kuma waxanda aka hangi za su taso. Tun kafin mulkin siyasa ya zo, suna amfani da rahotonni na fili da na sirri da suke samu wajen tattauna matsalolin jama'arsu a majalisarsu sannan kuma su sa ido sosai sai Turawan mulki sun xauki matakan da suka dace akan waxannan matsalolin ko masifu da ke addabar jama'a. Ana iya ba da wani misali da matsalar sayar da abinci da kayayyakin masarufi da ke damun jama'ar Arewa a shekarar 1949.

A zaman da Majalisar Sarakuna ta yi da Gwamna na ran 13 ga Nuwambar shekarar 1949 ne, Mai girma Sarkin Kano Abdullahi Bayero ya kawo matsalar boye kayayyakin abinci da 'yan kasuwa ke yi ga Majalisa domin a xauki matakin maganinta. A wannan zaman Majalisa, sai Sarkin ya ce:

"Halin voye hatsi domin a sayar da shi da tsada, ya kaucewa tsarin Addinmu yana kuma da illa babba ga jama'armu. Na sami qorafe-qorafe masu yawa akan wannan mugun hali saboda haka na kawo wannan matsala gaban Majalisa."[1] Nan da nan sai Sarkin Zazzau Jafaru shi ma ya fito fili ya bayyana jama'ar da ke aikata wannan mummunar sana'ar ya ce: "A shari'ar musulunci, wannan matsalar da muke tattaunawa haramunce . . ." Ya qara da cewa, "Ba mutanenmu ke aikata wannan muguwar sana'a ba 'yan Kudu da Qwarori wato Lebanese su ke aikata wannan muguwar sana'a. Su kan sai hatsi da araha, su saya su boye shi domin su sayar da shi da tsada a lokacin da farashin sa ya qaru, ko kuma su kai wasu larduna su sayar da tsaxa." Yana gama bayani, sai Sarkin Misau ya ba da shaidar cewa, "Gaskiya ne 'yan Kudu da Qwarori ke sayan hatsi da yawa don su kai wasu wuraren da za su ci muguwar riba. Ya kamata lallai, gwamnati ta xauki matakan maganin wannan matsala."[2]

---

1 *Northern House of Chiefs, Debates*, September 13, 1949, shafi na 4.

2 *Ibid*.

A wancan zamani Sarakuna sun san duk matsalolin jama'a da halin jama'a da yadda harkokin sana'arsu da yadda kasuwancinsu ke tafiya. Saboda haka a kusan faxin qasar mulkinsu, sun san aikace-aikacen 'yan Kudu da Qwarori, ta hanyar masu Unguwanni da Dagatai da Hakimai, a bisa wani irin tsarin mulki wanda tasirinsa ke da amfani har yanzu. Mulkinsu kuma ya shafi kowane mutum da addininsa, da sana'arsa, da halayyarsa. Saboda haka ba su gushe ba sai da suka maida jama'arsu masu halin qwarai. Musamman wajen nuna gaskiya da riqon amana, da sune kan gaba wajen ci da guminsu.

Tasirin Aiki da Ibada

A dukkan qasashen duniya a kan sami gwarzaye waxanda suka shahara a cikin al'umma wajen jan ragamar jama'arsu zuwa ga tudun na tsira, a lokacin da al'amari ya yi muni. Ga jama'ar Arewa kuwa, Sardauna ne ya yi abubuwa gagara-koya, ya kuma zama gade-bago a tarihin Arewa har ya zuwa wannan zamani kamar yadda Mahatma Ghandi yake ga qasar Indiya, haka Sir Ahmadu Bello yake ga Arewa. Kamar yadda Wilson Churchill yake ga qasar Ingila, haka Sardauna yake ga Arewa. Haka kuma kamar yadda John F. Kennedy yake ga qasar Amurka, haka Gamji Xan Qwarai yake ga Arewa.

Kafin Sardauna ya zamaFirimiya a shekarar 1954, an bar Arewa a baya a kusan duk harkokin sha'anin rayuwa a Nijeriya. Amma mutanen da aka bar su suna barci har da minshari, sai ga Sardauna ya farkar da su ya kumafidda su daga kutingwilolin hana ci gaba da aka garqama masu. Har kuma ga su, ana fafatawa da su a cikin harkokin Nijeriya a cikin shekaru goma sha-biyu kacal da mulkin sa.

Da wuya a sami qasar da aka yi wa irin wannan mummunar danniya, kamar Arewa a zamanin Mulkin Mallaka. A wannan lokaci ne aka taxiye ta aka kuma titsiyeta sannan aka washe arziqinta don a maida ta ita fankarfayo. Amma ina! Allah cikin Rahamarsa sai ya kawo Sir Ahmadu Bello wanda ya zo da Siyasa tabbatacciya. Siyasa da Sarakuna, wato siyasar kawo ci gaban al'umma ta kowa ne fanni. Ya kuma yi jagorar rundunar 'yan Siyasar Gaskiya, waxanda suka taru suka fidda Arewa daga cikin mummunan qangi. Amma ba su tsayanan ba, sai da suka kai ta, da taimakon Allah (SWT) ga matsayinta na martaba da daraja. Sai da suka maida Arewa wata qasa qi-faxi. Babu shakka wannan taimako ne daga Allah Mai Jinqai da Rahama. Sardauna ya xauki matakai biyu manya wajen cima nasara, kowane mataki na da rassa masu yawa.

Na farko, shi ne Aiki da Ibada. Na biyu kuma shi ne gwagwarmayar, "Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa," ya kuma jajircewajen ganin hakan ya yiwu. A bisa hankali da shari'a xan Arewa ne ya fi cancanta da ya nuna kishi da son ci gaban mutanen Arewa. Ibada ke kan gaba. Don haka yasa kirarin Jihar Arewa, "Aiki da Ibada. Amma Aiki da Ibada ba zai yiwu ba sai da karatu. Wannan ya sa Sardauna ya tanadi makarantu da masana'antu da wuraren Ibada waxanda jama'ar garin

Kaduna suka amfana da su, sannan mutanen Arewa kuma suka samu madafar ci gaba. Ya cewannan kirari wani abu ne wanda za a rayu a kai, ka bayar, ka tsare mutane a cikin kowane lokaci.[1]

Garin Kaduna shi ne cibiyar yaxa falsafar wannan take da aiwatar da siyasa da Sarakuna a Arewa. Firimiya ya bayyanata ta wannan hanya a mujallar KAI da 'yancin Nijeriya: "Duk da tsofaffin al'adunmu, da ci gaban mu a cikin sha'anonin zamani, qaramar qasa, ba tare da aiki mai wuya ba, da kuma qoqari wajen aiki, ba za mu yi fatar samun qasashe ba, waxanda ke gaba da mu wajen lafiya, arziqi da kuma jin daxi na mutanensu. Amma aiki sosai shi kansa zai ba mu riba kaxan, sai fa in mun ci gaba da qarfafa addinin da muke bi, da xa'a da kuma gaskiya tare da adalci."[2]

Babu shakka wasu ginshiqan ci gaban kowace al'ummasu ne: Aiki da Ibada, waxanda su ne za su haifar da xa'a da gaskiya tare da adalci. Haka kuma matasa su ne ginshiqan ci gaba, musamman waxanda suka samu horo da kyawawan al'adu da ta'adu. Don haka ne ya jajircewajen cunkusa aqidar Aiki da Ibada a zukatan matasa.

Garin Kaduna ya bunqasa da manyan ayyukan da Sardauna ya kawo wajen ganin samari sun himmatu sun kuma ginu a kan aqidar Aiki da Ibada. Wannan kyakkyawar aqida ta kafu sosai bayan Jihar Arewa ta zama mai mulkin kanta ran 15 ga watan Maris xin shekarar 1959. Tun fil a zal, mutanen Arewa ba sa wasa da Ibadar su da aikinsu. Da waxannan halaye su ka yi fice a duniya. Tun daga wannan lokaci Kaduna ta ci gaba da bunqasa da makarantu da masana'antu saboda jajircewar Sir Ahmadu Bello da ya yi wajen ganin samari sun sami ilimi da koyon sana'a. Ko da Tarayyar Nijeriya ta sami 'yanci, kuma ta shiga qasashen da ke aminci da Ingila, ran 1 ga Oktoban shekarar 1960, garin Kaduna ya riga ya havaka sosai da gine-gine a matsayinsa na farfijiyar Arewa.

Kaduna ta samu manyan makarantu da cibiyoyin qaro ilimi na qasa da kuma manyan masana'antu, kamar masaqun kaxi da saqa na auduga da wurin yin abubuwan sha na zaqi, da wurin yin katako na zamani da xaba'i. Haka kuma, akwai makarantar horar da mataimakan Likitoci da masu Haxa magani da Nas-Nas maza da mata da kuma unguwarzoma.

A fannin ilimi har yanzu ba a bar Kaduna a baya ba, ayyukan Sardauna sun yi tasiri sosai a wannan gari. Akwai Cibiyar Bincike Akan Kuxan Tsando Ta Qasa wato *National Institute for Trypanosomiasis Research Centre* (NITR) da Cibiyar da ke Kula da Ilimin 'Ya'yan Makiyaya ta qasa, *National Commission for Nomadic Education* da cibiyar kula da Malamai wato *National Teachers' Institute* ta qasa da cibiyar da ke kula da Sana'a ta qasa wato *National Board for Technical*

---

[1] *Kai da 'Yancin Nijeriya*, shafi na 2.

[2] *Ibid*. shafi na 2.

Education da cibiyar da ke kula da ilimin Firamare ta qasa wato *National Primary Education Commission* da makamantansu. Ga Kwalejin Koyon tuqin jirgin sama a Zariya, wato *School of Aviation*.

Sardauna ya tsare Arewa don 'yan Arewa, ya kuma hango cewa babu yadda za su ci ribar wannan jiha mai albarka da qasa baki xaya sai sun riqe Aiki da Ibada da hannu bibbiyu. Im ba haka ba 'yan Arewa za su zama bayi a qasarsu ta haihuwa domin 'yan Kudu za su zo su mallake su, su kuma maida su qyale qyale huhun-ma'ahu! Firimiya bai yi sakaci wajen farkar da jama'arsa ba, saboda qalubalen da zai fuskanci wannan jiha anan gaba. A dalilin haka ne ya yi kira ga samari.

Ga abin da ya ce: "Kun rayu a cikin zamani mai tashin hankali," yaci gaba da cewa, "Qasarmu ta fita daga duhu ta shiga cikin haske. Kuna tsaye a kan tudu na nasara don ku sami cikakkiyar dama."[1] Waxansu kalmomi masu faxakarwa waxanda suka cancanci ambato su ne cewa samari sun rayu a cikin zamani mai tashin hankali. Alal haqiqa, wannan zamani na mu a yanzu ya fi kowane zamani tashin hankali, rayuwa kuma a cikinsa tafi wuya da haxari fiye da na kowa ne zamani da ya shuxe. Kiran da Sardauna ya yi ga samarin Arewa ya dace sosai ga samarin wannan zamani na mu a yau. Kowa ce Al'umma na ci gaba idan matasanta suka sami dama da ikon cimma muradinsu a harkokin rayuwa daban-daban. Akan samu hakan, idan wannan al'umma ta samu kyakyawan shugabanci ta kuma ginu akan aqidar Aiki Da Ibada.

Amma haxarin zamani ba zai kawo mummunan barazana ga samari da matasa ba, in sun *xauki* cewa qalubalen zamani wata jarabawa ce a gare su, da za su kuma ba da hankulansu ga aiki tuquru don ci gabansu da na qasarsu baki xaya. Sardauna ya ce: "Kowa ne matashi ya tambayi kansa: Kai kam ka xan tava tsayawa, ka yi tunani, kuma ka tambayi kanka, me ka yi wa qasarku wanda zai sa ta qara girma? "Kada kawai ka ce kana xaya daga cikin miliyoyin mutane, ka ci gaba da tunatar da kowane daga cikinmu, ci gaba, da jin daxin qasa ya danganta a kan kowane mutum, akan yaqinsu na taimakon kai, da kishin zuci don qaruwar arziqin qasa."

A cikin wannan gwagwarmayar, samari ba za su iyawa su ka xai ba sai sun sami taimako daga dattawansu, sai kuma shugabanni sun kai su ga tudun nasara don su sami cikakkiyar dama. Sardauna ya yi yaqi tuquru wajen korar halin bara da tumasanci daga zukatan 'yan Arewa. Don kuwa idan waxannan miyagun halaye suka yi katutu a zukatan 'yan Arewa, to, shirinsa na Aiki da Ibada, da Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa za su ci tura. 'Yan Kudu kuma za su mallake wannan jiha mai albarka. Saboda gudun haka ne ya yi hovvasa wajen baiwa matasa cikakkiyar dama. Gina makarantu da masana'antu suna daga cikin cikakkiyar dama da Sardauna ya baiwa matasan Arewa.

---

[1] *Kai da 'Yancin Nijeriya*, shafi na shafi na 1

Ita duniya a kullum cikin tashin hankali take. Zamanta ba shi da daxi saboda rashin tabbataccin rawuya. Don haka ne a ke wa duniya kirarin, "auranki sai gwani." Akan ce kuma "duniya bata ga raggo." Amma kuma maganinta sahihi shi ne Aiki da Ibada. Sardauna ya bayyan wannan falsafa filla-filla, ya kuma nuna aiki da misali. Don bai tsaya gina masallatai ba sai da ya haxa da gina makarantu da masana'antu don baiwa matasa wata dama da garkuwa, a gwagwarmayar yaqin neman wanzuwa a cikin zamani mai cike da tashin hakali. A zamaninsa Arewa ta samu bunqasar masana'antu. Don aqidar Aiki da Ibada ta tasirantu akan jama'ar Arewa.

Bunqasar Masana'antu

Sir Ahmadu Bello gawurtaccen maginin al'umma ne ya lura da cewa, aiki ba zai yiwu ba sai da wurin yin sa, wato ma'aikatu da masana'antu. Wannan ya sa ya xauki matakan bunqasa masana'antu a Arewa waxanda suke a garuruwan Kaduna da Kano da Ilori da sauran sassan wannan Jiha.

Arewa ta sami bunqasar kamfanoni da ma'aikatu ne bayan qarshen yaqin duniya na biyu daga shekarar 1946 zuwa shekarar 1963. An kuma shirya cimma wannan bunqasa ce a rukunai guda uku, da aka xauka bi da bi, wato rukuni na bayan yaqi, da matsakaicin lokaci, da lokacin bunqasar arziqi.

Daga Shekarar 1946 zuwa 1954: Ba a sami ci gaban bunqasa masana'antu ba a wannan lokaci, saboda wahalhalun da duniya ta shiga a qarshen yaqin duniya na biyu. Wannan ya haifar da tsadar kayayyakin gine-gine. Amma an samu bunqasar Ma'aikatar Arewa, wato *Northern Nigerian Industry* a wannan lokaci, musamman ta fannin haqar kuza da ma'aikatar Matsar Mai wato *Oilseed Crushing Industries*. A hankali sai aka riqa samun sauqin al'amuran qasa.

A Matsakaicin Lokaci:- Shekarar 1955 zuwa 1959, a wannan lokaci an samu qarin ma'aikatu. A wannan zamani ne ma Arewa ta sami mulkin kai, a watan Maris na shekarar 1959. An lura da cewa idan ana son bunqasar masana'antu sai an sami nasara wajen samar da kuxaxe da qwararru daga qetare, sai kuma an sayo kayayyakin aiki. Sir Ahmadu Bello ya bayyana shirinsa a lokacin samun mulkin kai na Arewa inda ya ce: "gwamnati ta lura da amfani da muhimmancin qasashen waje, wajen samar da qwararrun ma'aikata don faxaxa tattalin arziqin Jihar Arewa. Mun karvi wasu masana'antu daga qetare waxanda jarinsu da himmarsu da qwarewarsu za su taimaka gaya wajen ci gaban Arewa, musamman waxanda ke da burin haxin gwiwa da 'yan qasa. Ba mu yarda da mu daddage wajen harkar tu'amuli da kasuwanci na hannun 'yan qasa kawai ba, amma a shirye muke mu yi na'am da shirye-shirye ko shawarwari masu kyau da za su ba da damar xaukar ma'aikata da horar da su don ci gaban wannan Jiha."

Arewar Nijeriya ta samu bunqasar masana'antu ne a cikin shekaru biyar, daga shekarar 1955 zuwa 1959 saboda cimma yarjejeniyar da aka samu damar yi da

masu masana'antu saqa daga Ingila da suka yarda za su gina babbar masaqa a Kaduna. An sa hannun wannan yarjejeniyar da su a shekarar 1955. Amma a cikin shekaru biyu kacal, sai ga shi har an kammala gina katafariyar masaqa. A cikin watan Nuwamban shekarar 1957, Firimiyan Jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello Sardauna, ya buxeta cikin nasara. Nan da nan sai arziqin masana'antu ya shiga bunqasa sosai.

A Shekarun 1960 zuwa 1963, Arewa ta shiga shekarar da aka samu 'Yancin Kai. An sami xan cikas wajen bunqasar masana'antu saboda fahimtar da aka yi da cewa, in ana son samun faxaxar arziqin masana'antu, ya kamata kamfanoni da masana'antu su riqa samun kayayyakin sarrafawa daga Arewa, amma ba daga qetare ba. An kuma hango amfanin saka hannun jarin 'yan kasuwa, musamman daga qasashen wajen zai taimaka wajen bunqasa tattalin arziqin waxannan masana'anatu.

Don haka sai aka xauki matakan ganin an sami masu saka jarinsu da ganin kuma akwai shiri mai kyau da zai ga 'yan Arewa an ba su horo don su riqe manyan muqamai a waxannan masana'antu. Bayan samun mulkin kai ran xaya ga watan Oktoban shekarar 1960, Jihar Arewa sai ta zama qasa wadda ake son a shigo da injuna da kayayyakin aiki cikinta don zuba jarin kafa masana'antu.

Saboda samun havakar da masana'antu suka samu ne, sai ya zama wajibi a faxaxa wuraren kafa su. Don haka ne aka yi shirin kafa kamfanoni da masana'antu a garuruwan Sakkwato da Gusau da Maiduguri da Ilori da kuma Gombe. Haka kuma an samu qarin masana'antu a garin Kaduna a shekarar 1962. Don haka sai aka qara faxaxa Unguwar Masana'antu da ke Kakuri a Kaduna.

gwamnatin Jihar Arewa ta so ta kafa masana'antu ba a gari guda ba amma a duk fadin Jihar xaya, amma sai akai la'akari da akwai abubuwan dubawa kafin a kafa su. Kamar samar da kayayyakin sarrafawa da raba kayayyakin da aka sarrafa cikin gaggawa ga jama'a. Garin Kaduna ya samu kafuwar masana'antu masu yawa saboda garin na da isassun hanyoyin mota da hanyar jirgin qasa waxanda za su taimaka wajen raba kayayyakin da aka sarrafa ga duk faxin Nijeriya.

Idan ana son aqidar Aiki da Ibada ta tasirantu akan 'yan Arewa, to, ya zama wajibi a buxe masu wasu kafafen samun tallafin kuxi rance domin bunqasar kasuwanci da kamfanoni. A dalilin haka ne Sardauna ya buxe Bankin Arewa wato *Bank of the North* a birnin Kano da wasu bankuna a sassan Arewa. Saboda sai 'yan qasa na da qarfin arziqi ne za su iya jawo hankalin masu zuba jari daga qetare don havaka masana'antu, da kasuwanci da kamfanoni.

Bankin Arewa

Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato ya buxe Bankin 'Yan Qasa wato Bankin Arewa, a Kano a gaban muhimman mutanen da aka gayyata da kuma 'yan kallo kamar dubu biyu. A cikin manyan mutanen da suka halarci wajen bikin buxe wannan banki, har da Alhaji Muhammadu Ribaxu, Ministan Al'amuran Ikko na Nijeriya, da Alhaji Inuwa Wada Kano, Ministan Ayyuka na Nijeriya da Mr. R. E. Greswell, babban Razdan na Kano.

Ban da waxannan kuma, akwai Alhaji Mustafa Monguno, Ministan Aikin Gona na Jihar Arewa, da Alhaji MaiKano Dutse, Ministan Mulkin En'e na Jihar Arewa, M. Shehu Usman Galadiman Maska, Ministan Kula da Sha'anin Gida na Jihar Arewa, da Alhaji Ahman Galadiman Pategi, Ministan Lafiya na Jihar Arewa, da M. Abba Habib, Ministan Ciniki da Sana'o'i na Jihar Arewa, da Alhaji Aliyu Turakin Zazzau, Shugaban Kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa kuma xaya daga cikin Darektocin bankin, da Alhaji Ado Sanusi Xantata, wanda yake shi ma yana cikin Darektocin bankin. Cikin manyan 'yan kasuwa kuma, akwai Mr. S. Raccah, da Daraktan Kamfanin Mandridis, da Mr. Balwin da Mr. Karouni da sauransu jingim. Kafin Sarkin Kano, Alhaji Sir Muhammadu Sanusi ya kira Firimiya ya buxe wannan banki, sai da ya yi jawabi ya ce: *"wannan biki da muka zo yi, muhimmin abu ne game da tarihin Kano kuma kamar yadda aka sani, Kano an santa a kan sha'anin ciniki da sana'o'i.*

"Shekaru xaruruwa da suka wuce mutane sun zo daga qasashen Turai da qetaren Sahara saboda saye da sayarwa a Kano. Kuma tun can da sana'o'in hannummu suna xaya daga cikin abin alfaharimmu, sa'an nan daga baya muka qara samun sabbin sana'o'i daga sashen Turai. Waxannan aikace-aikacen duk ba za a iya tafiyar da su ba sosai sai da sha'anin taimako game da rance. Ko da yake abin da muka riga muka sani ne yin rance da ba da rance abin da aka saba yine.

A yanzu bankunan Turawa sun fito da hanyar taimakon jama'a ko da yake ba su iya gauraya ko'ina ba. Kuma duk da haka ana buqatar kuxi dunqulallu da za a iya tafiyar da sana'o'i da kuma sana'o'in ci gaban qasa. A kan wannan ne dukammu a Kano muke matuqar farin ciki da samun wannan banki."[1]

Bayan da Sarkin Kano ya qare jawabinsa, sai ya kira Firimiya don ya buxe bankin. Amma kafin ya buxe bankin, sai da Xan'iyan Kano ya fassara jawabin Sarkin Kano cikin Turanci. Bayan ya gama ne, sa'an nan Firimiya ya yi nasa jawabin cikin Hausa da Turanci. A ciki Firimiya ya ce:

[1] GTK 15/1/1960, shafi na 12

"Wannan babbar rana ce game da tarihin Nijeriya ta Arewa. Wannan banki, shi ne na farko a Jihar Arewa kuma shi ne ainihin bankin 'yan qasa wanda 'yan Arewa suka yi na kansu.

Da ma kowa ya sani Kano babban gari ne mai cike da tarihi game da sha'anin ciniki. Shekaru masu yawan gaske da suka wuce mutane sun zo daga qetaren teku don ciniki a Kano. Saboda haka ba abin mamaki ba ne idan wani muhimmin abu game da sha'anin ciniki aka same shi a Kano. Turawa su suka soma kawo sha'anin banki, amma wannan bankin zai yi gogayya da su in sha Allahu."[1]

A zuwa qarshen jawabinsa, sai ya ce sha'anin banki abu ne mai buqatar gaskiya da aminci har abada, kuma ya yi fatan samun waxanda za su tafiyar da aikin bankin ba tare da kasala ba. Ya qare da fatan Allah Ya sa albarka kuma ya zama ana samun riba ba faxuwa ba daga bankin. Da ya gama jawabinsa, sai ya yanke kirtanin, da ke nuna alamar buxe bankin.

A cikin nasa jawabin da ya yi wa 'yan jaridu kuwa kafin a buxe bankin, Mr. Ali Arab, Daraktan Bankin ya ce shekara da shekaru bankunan Turawa ke tafiyar da sha'anin banki a Jihar Arewa, domin su ne na farko wajen ajiye wa gwamnati da kantuna manya da qanana kuxi da sauran abubuwa na game da banki. Ya ce:

"Ko ba don ba da rance ba wanda yake ba mai xaukar dogon lokaci ba, waxannan bankuna ba su saki jiki ba wajen sanya kuxaxensu kan qananan sana'o'i. Amma ga shi yanzu abin duk ya canja. Tun wata doka da aka kafa a cikin shekarar 1952 wadda ta ba Sakataren Kuxi na gwamnatin Nijeriya ikon kula da abin da zai amfani jama'a, tun lokacin jama'a da 'yan kasuwa da manoma da masu sana'ar hannu suka soma fahintar amfanin banki.

Haka kuma bankuna da ganin irin marabar da jama'a suka yi musu, sai suka shiga buxe rassa a manyan garuruwa a Arewa. Wannan kuwa tabbatacciyar magana ce tun da arziqin Arewa na qaruwa. Saboda haka abu ne wanda zai zama muhimmi da zai amfani Arewa fiye da yadda a ke zato idan ta sami bankin kanta wanda zai dace da al'adunta.

A kan wannan ne aka yi shawarwari kafa wannan Bankin Arewa wanda zai ba jama'ar Arewa damar ajiya, kuma ya sa kuxaxe cikin waxansu sana'o'i ko aikace-aikace sabbi ko kuma waxanda su ke akwai su tun tuni."[2]

---

1 GTK, 15/1/1960, shafi na 12

2 *Ibid.*

Buxe Reshen Bankin 'Yan Qasa a Kaduna

Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello ya sake buxe reshen Bankin 'Yan Qasa na biyu a Kaduna, a wani qasaitaccen biki da aka yi a Ofishin Kamfanin Raya Qasa. Ga jawabin Firimiya a wurin buxe Bankin:

Kamar mako xaya ke nan da ya wuce aka rubuta babi na farko game da labarin tanadi na Jihar Arewa a Kano, lokacin da na buxe bankin 'Yan qasa na farko a Kano.

Mun sake taruwa yau kuma don buxe wani bankin, wato reshen wannan banki a nan Kaduna. Wannan kuwa shi ne reshe na farko daga cikin rassan da za a buxe ba da jimawa ba a Ikko, da Jos, da Maiduguri, da waxansu muhimman wuraren ciniki a Jihar Arewa.

Kwanakin nan Kaduna ba Hedkwatar Jihar Arewa kaxai take ba, har ma ta zama wuri wanda ya dace da manyan ma'aikatan sana'o'i. Ganin Masaqar Kaduna da sauran makamantansu sun isa abin ishara. Kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa ko yaushe cikin hidima yake game da buxe sabbin hanyoyi, kwalbati da shirin gina waxansu gidaje a Kaduna Jamsin duk don jawo Hankalin 'yan kasuwa.

Wani abu kuma wanda zai qara shaharar Kaduna kamar yadda ku ke jim shi ne hotel wanda za a gina. Wannan ba da jimawa ba za a fara gininsa. Muna shirin gina waxansu wurare da dama.

Wannan banki da aka buxe yau, yanzu zai riqa aiki a nan Kamfanin Raya Qasa har kafin a gina ofishi musamman wanda za a tafiyar da ayyukan bankin cikinsa. Yanzu abin da bankin ke da shi, shi ne £250,000. waxannan kuxaxe kuwa, Kamfanin Raya Qasa, Hukumar Ciniki ta Jihar Arewa, da wasu 'yan qasa ne suka tara shi. Babbar manufar wannan banki ita ce inganta ba da rance kamar yadda sauran bankuna na Nijeriyake yi.

A wannan lokaci kuma, zan sake faxin abin da na ce a lokacin da na yi jawabin buxe babban wannan banki a Kano. Sha'anin banki, wata harka cewadda ke buqatar kyawawan halaye da nagarta nagari, kuma na tabbata ko yaushe za a samu mutanen da suka cancanta su tafiyar da sha'anin wannan banki. Na tabbata da taimakon Allah wannan banki zai yi aikinsa wanda zai kai wannan qasa tamu ga samun nasara." Daga nan sai Firimiyan ya buxe bankin.[1]

[1] GTK, 22/1/1960

Kamfanin NNDC

Ta fuskar bunqasa tattalin arziqin mutanen Arewa sai Sardauna ya taimaka wajen kafa Bankin Arewa wato *Bank of the North*. Ya kuma jajirce da ganin wannan banki ya kafu sosai shekarar 1959. An kafa kamfanin *Northern Regional Production Development Corporation* (NRPDC) a shekarar 1949. Amma da samun mulkin kai a shekarar 1960 sai aka sauya wa wannan kamfani suna zuwa *Northern Nigeria Development Company* (NNDC) aka kuma bunqasashi don ya ci gaba da lura da kuma bunqasa kadarorin Jihar Arewa.

Babu shakka kamfanoni da masana'antu sun taimakawa matasa wajen samar masu da ayyuka don haka sun taimaka gaya wajen tabbatar aqidar Aiki da Ibada ta yaxu a Arewa. A na kuma sa ran wannan aqidar ta qara qarfi da yaxuwa don idan kamfanoni da masana'antu suka inganta za su baiwa 'yan Arewa sana'o'i da ayyuka saboda musulunci ya hana bara da zaman banza, da tumasanci.

Kamar kowane muhimmin vangare na gwamnati, Kamfanin Raya Kadarorin Arewa wato NNDC ya zama sabon tsarin sufuri na qarni na ashirin na sabuwar Arewa wanda a halin yanzu ya zama jagoran sauran sassan qasar nan a vangaren ci gaban Masana'antu. NNDC shi ne babba a hukumomi na gwamnati waxanda aikace-aikacensu ke da tasirin gaske da kuma dai-dai da bunqasar ci gaban tattalin yankin Arewa da samar da ayyukan yi ga miliyoyin jama'a da xora qasa a tuvar ci gaban masana'antu. NNDC ginshiqi ne a tseren ci gaban masana'antu da a yau xin nan bai kai shekaru xari ba da kafa shi ya zama tubalin gina sabuwar alqiblar ci gaban masana'antu.

Kamfanin NNDC, kamfani ne wanda yake da jarin na miliyoyin nairori wanda yake da alhakkin samar da kuxaxe da gudanar da Masana'antu masu yawa kuma da ke warwatse a ko'ina a yankin Arewa, da kuma ba da shawarwari na qwararru ga vangaren kuxi da makamantansu ga 'yan Arewa da dama da ke tasowa kuma ke cikin harkar kasuwanci.

Kuma wata gagarumar nasara ita ce a cikin xan qanqanen lokaci da kafa kamfani na NNDC, a wancan zamani zai iya tinqahon cewa yana riqe da wasu masana'antu guda hamsin da ke sassa daban-daban na Arewa. Kamar yadda rahoton kamfanin ke nunawa sabon Shugaban Kamfanin Alhaji Muhammadu Ladan wanda ba a daxe da tabbatar masa da wannan muqamin ya yi riqon qwarya na shekaru uku, a jawabinsa na duba qwazon kamfanin daga shekara ta 1962 zuwa 1963 ya yi bayanin cewa tsarin kamfanin NNDC na nan bai sauya ba, wato amfani da kuxaxensa wajen rayawa da kuma faxaxa tattalin arziqin Arewa.

Sai dai saboda xinbin ayyukan da ke gabansa sannan ga aljihun babu nauyi sosai, kuxaxen da ake turawa wasu ma'aikatu a matsayin gudunmawar kamfanin ga kafawa ko xorewar wasu ayyuka na ci gaba da kuma faxaxawa a vangarorin aikin gona da kiwo, da samar da ruwa da tattalin qasar noma, ko dai a rage tallafin da ake ba da wa a waxannan vangarori ko kuma a dakatar da tallafin gaba xaya.

Sai dai abin farantawa shi ne ya kamata a lura cewa da dama daga cikin waxancan tsare-tsare da aikace-aikace, sun rigaya sun kafu kafin wannan al'amari; saboda haka babu wata koma baya da suka samu, sakamakon rashin samar da wasu kuxaxen ko a wasu lokutan kuxin sun ragu.

Kuxaxen da ake da su an ci gaba da zuba su a fannoni daban-daban na masana'antu da ke da riba da kuma aikace-aikace. Kuma an ba da jerinsu a cikin wannan nazari. Tsarin da ya shafi samar da kuxaxe ga hanyoyi na nan bai canza ba kuma kuxaxen da aka bayar na wannan mataki na ran da za a gudanar da gine-ginen hanyoyin da su.

Kamfanin na ci gaba da xorewa da sha'awar da yake da ita a bincike daban-daban da ke da nasaba da kafa masana'antu na Siminti da Rama da Sikari, tare da haxin gwiwa ta qut-da-qut da Ma'aikatar Ciniki da Masana'antu da kuma musamman Ma'aikatar Aikin Gona.

Ta hanyar nacewa wajen binciken yiwuwar sabbin tsare-tsare da kuma shiga qawance da masu zuba jari daga qasashen qetare da kuma 'yan kasuwannimmu na nan cikin gida da kuma ba da basussuka ga 'yan kasuwa da masana'antu qanana da manya, kamfani na ci gaba da taka mihimmiyar rawa ga bunqasar tattalin arziqin Arewacin Nijeriya.

Kamfanin NNDC na nan yana ci gaba da zama akan gaba bisa kyakkyawar turba wanda wata nasara ce ga gwamnatin NPC. Ba ta tava yin qasa a gwiwa ba a qoqarin da take yi na sanya Arewa ta zama cikin qarin farin ciki da zama waje mai yalwa tamkar aljannar-duniya, da kowa zai so ya zauna da zama xanta. Za a iya gani daga bayanin da shugaba ya yi a game da kamanin cewa ya tavo kowace fuska ta dukkan ci gaba.

Qididdiga ta nuna cewa masana'antun da ko dai NNDC ya mallaki rabi da rabi ko gaba xayanta, na nan tana ci gaba babu kama hannnun yaro da riba mai qarfafa gwiwa. Jama'a sai ci gaba da qara samun aiki suke yi ba kaxan ba kuma akwai kyakkyawar dama ta faxaxa wannan ci gaba.

Za a wallafa bayanai dalla-dalla akan nasarar da kowace masana'anta ta samu.

Kamfanin da NNDC ke Raya Kadarorinsu sun haxa da:

1 Guinea Insurance Company Limited
2 Kano Citizen Trading Company Limited
3 Nigerian Creamers Limited
4 Sword Brand Bottling Company Limited
5 Nothern Construction Company Limited
6 Kaduna Textiles Limited
7 Nigerian Canning Company Limited
8 Thomas Wyatt and Sons (Nothern Nigeria) Limited
9 Arabs Transport (Nothern Nigeria) Limited

10 Northex Nigeria Limited
11 Niger Marine Engineering Company Limited
12 Northern Deveopment (Nigeria) Limited
13 Bank of the North Limited
14 Association Traction (Northern Nigeria) Limited
15 Nigerian Sweet Confectionary Company Limited
16 A.B Properties Limited
17 Holt Nigerian Tanneries Limited
18 Nothern Enamelware Company Limited
19 Tahir Brother Limited
20 E.M.I (Nigeria) Limited
21 Nigerian Carbon Dioxide Company Limited
22 Minna Pig Farm Limited[1]

Hannayen Jarin Kamfanin NNDC wannan kamfani na da hannayen jari a waxannan Kamfanoni da Masana'antu:

S/N	Kamfanoni	Jari
1	A.B Properties	£300,00
2	Ahmad K. Ahmad Farm Bakura	£45,000
3	Bank of the North Limited	£125,000
4	Bauchi N.A Market Stalls	£5,000
5	Bauchi N.A Street Lightings	£9,310
6	Kaduna Hotels Limited	£188,935
7	Kano Abbatoir	£10,000 Equity £80,00 loan
8	Katsina N.A Malumfashi Motor Park	£3,500
9	Minna Farm Limited (Piggery)	£7,000 Equity £12,000 Loan
10	Nasarawa N.A Haxari River Bridge	£5,576
11	Nigerian Creameries Limited	£107,000
12	Nigerian Leather Works Limited	£100,000
13	Nigerian Sugar Company Limited	£310,000
14	Niger Marine K. Engineering Company Limited	£40,000
15	Nortex (Nigeria) Limited	£70,000 Equity £40,000 Loan
16	Northern Garage Gusau	£25,000 Loan £6,000 Equity
17	Northern Development (Nigeria) Limited	£300,000 Equity

[1] Nigerian Citizen, Laraba, 8th July 1964, shafi na 8

18	Northern Enamelware Company Limited	£35,000 Equity £50,000 Loan
19	Sword Brand Bottling Company Limited	£50,000
20	Thomas Wyatt K Company (Northern Nigeria) Limited	£20,000
21	E.M.I Nigeria Limited	£23,000 [1]

Buxe Sabon Bankin Barclays

Jawabin Firimiyan Jihar Arewa, Mai girma Alhaji Ahmadu, C.B.E Sardaunan Sakkwato a lokacin buxe sabon ginin Bankin Barclays. (D.C.O) a Kaduna, a ranar 15 ga Satumba, 1956, ya ce:

Darakta,

Mata da Maza,

Ina mai matuqar farin ciki da aka gayyace ni in buxe wannan biki a yau a sabon ginin Bankin Barclays a Kaduna. A lokacin da na buxe asusun ajiyanawa na kaina a wannan banki, ban tava tunanin cewa ranar da zan buxe bankin shi kansa za ta zo ba. Amma ina mai matuqar farin cikin yin wannan biki, domin na yi amanna da cewa nan da shekaru masu zuwa, mutum zai tuna baya ya dubi wannan rana a matsayin tushen muhimmancin yankin Kaduna a matsayin cibiyar kasuwanci da qere-qere. A yau ga sabon ofishin banki ana buxewa. Daura da shi wani bankin ne ana ginawa. Ana iya hango sabbin ofisoshin kasuwancinsa sun miqe sama daga kan titin Prince Edward.

Can gaba da su kuma ga sabbin kantuna da garajen motoci da gidajen mai. A gefen Kudu kuma ga katafariyar masaqa an kusa gamawa, an kuma fara ayyuka a kan sauran masana'antu. Ni abin alfahari ne a gareni cewa dukkan waxannan ayyuka sun samu ne a lokacin da nake shugabanci.

Lord Lugga da yana nan, da ya yi murna ya ga waxannan ayyukan ci-gaba a cibiyar mulkin da ya zava. Mutanen lardin Arewa ko shakka babu, za su yi murna su ga babban birninsu yana girma a muhimmanci babu kama hannun yaro ta fuskar mulki da kasuwanci da kuma qere-qere.

Bankin Barclays ya shigo Afirka ta Yamma a karon farko a shekarar 1917 a lokacin Yaqin Duniya. A lokacin da aka gama Yaqin Duniya na qarshe bankin na da rassa 17 a faxin dukkan Afirka ta Yamma. Amma a yau, adadin ya sha bamban nesa ba kusa ba. A cikin

[1] Nigerian Citizen, Laraba, 8th July 1964, shafi na 8

shekara goma da ta wuce, bankin ya faxaxa ayukansa matuqa, ta yadda a yanzu yana da rassa 73 a Afirka ta Yamma. Wannan labari ne mai faranta rai, domin ya nuna cewa, idan bankin da ya kama qasa irin Barclays a shirye yake ya faxaxa ayyukansa cikin gaggawa a ko'ina, to sauran kamfanonin kasuwanci na waje, za su saki jikinsu da qasashen Afirka ta Yamma. Sakin jikin na nufin qaruwar qwararrun ma'aikata, da zuba jari da kamfanonin waje za su yi, abin da wannan qasa ke buqata cikin gaggawa. Idan kuwa na cewannan qasa, ina nufin dukkan Nijeriya.

Wani muhimmin abu da ya auku a harkar Barclays, wanda ne a wurina shi ne mafi muhimmanci, shi ne ya auku a (qasar) Ghana a bana. Bankin ya buxe sabon ofishin lardi a Accra a watan Yuni, domin ya riqa duba Ofisoshin Bankin a Ghana da Sierra Leone. Tun daga shekarar 1951, waxannan ofisoshi suna qarqashin ofishin Lagos ne, kuma kafin shekarar 1951, kowanne reshe yana qarqashin London ne." Ko me ya sa zan xauki wannan a matsayin muhimmin abu? Akwai dalilai biyu:

***Na xaya** shi ne Bankin Barclays na nuna wa duniya cewa ya lura da yadda tattalin arziqi da hada-hadar kasuwancin yankunan Afirka ta Yamma ke bunqasa. A yau akwai ofisoshin lardi guda biyu, a inda a 'yan shekaru kaxan baya, babu ko xaya.*

***Na biyu** ya nuna cewa Bankin Barclays ya gane muhammancin faxaxawa. Wato, damqa wa shugabanni cikakken iko a inda suke, waxanda kuma su ne ke da ilimin hali da buqatun mutanen wurin.*

Shekaru da dama da suka shuxe, ofisoshin da ke nesa da qasarmu su ne suka riqa tafiyar da harkokin kasuwancin qasashen waje. Cibiyoyin ofisoshi a London da Manchester da Paris da Humburg da kuma Switzerland. Wannan takurawa ta hana mutumin da yake shi ne a wurin, mutumin da yake shi ne ya san halin da ake ciki, ya samu damar yin amfani da basirarsa, a samu bunqasa domin ci gabansa da ci-gaban mutunen wurin a lokuta da dama.

Ana xaukar lokacin kafin a iya yin magana da babban ofishi, waxanda suke nesa da inda ake yin aikin. A duniyar kuxi da kasuwanci lokaci kuxi ne, jin kuma yana nufin asara. Saboda haka ina mai fatar cewa saura za su yi koyi da Bankin Barclays kan faxaxawa.

Haka kuma ina mai qaunar fatar arziqinmu ya bunqasa, ta yadda za mu ga qarin rassan bankin Barclays a lardin Arewa ta yadda nan gaba kaxan za mu sami ofishin lardi a Kaduna, domin rassan da ake da su a yankin. Haka kuma, ina son in ga mutane da dama suna aiki da Bankin Barclays - mutune nagari masu hazaqa, waxanda za su

tallafa lardin yaci gajiyar bankin, haka kuma ni da abokan aikina, za mu yi iyakar qoqarinmu, mu ga cewa mutanenmu sun fahimci amfanin Bankunan kasuwanci.

A halin da ake ciki, ina taya Bankin murnar faxaxa ayyukansa, musamman ma waxannan sabbin gine-gine a Kaduna.

Ina roqon Allah Ya sanya farin ciki da hamdala ga duk waxanda suke aiki a nan, da kuma waxanda suke kasuwanci a wurin.[1]

Sir Ahmadu Bello qasaitaccen mutum wanda ya qware ya kuma goge a harkar mulki, shi kuma sakaina ne mai iya ruwa a harkar siyasa. Lafazinsa da jawabinsa na nuna cewa ya fahimci har kasuwancin cikin qasa da qetare. A kowane hali kuma bai kaucewa alqiblar da ya fuskanta. Domin ya cimman manufarsa ta cunkusawa jama'arsa aqidar Aiki da Ibada bai tsaya wajen gina masana'antu ba, ya jajircewajen taimakawa 'yan kasuwa baqi da 'yan qasa wajen buxe kamfanoni. Don qarin masana'antu da kamfanoni ne zai baiwa 'yan Arewa guraben aiki iri-iri, wanda ko shakka babu zai havaka arziqin wannan Jiha. A dalilin haka ne ma kamfanin J. Allen, wanda ya shahara wajen sayar da da motocin Ford, ya gayyaci Sardauna don buxe sabon xakin talla wato showroom da ta gina.

Buxe Xakin Tallan Kamfani J. Allen

Jawabin Firimiya a wajen bikin buxe Gareji da xakin talla na Kamfanin J. Allen a kan titin Prince Edward a Kaduna ranar Asabar, 21 ga Satumba 1957. Kamar kowane jawabinsa a cike yake da hikima da fahimtar makama. Ga jawabin Mai girma:

Shugaba, da Ministoci, da Sarakuna, da shugabannin ilimi, da kuma mata da maza. Ni ba baqo ne ba a wajen bikin qaddamarwa. A watan da ya wuce kaxai ma, sau biyu ina samun gatar in buxe wasu bukukuwa waxanda suna da taraiya ta qut-da-qut da harkar da za a qaddamar a nan a yau. Ina magana ne a kan gadar Kaduna da kuma tashar manyan motoci.

A wajen wannan biki da wasu bukukuwan na yi magana a kan bunqasar babban birninmu Kaduna. A yau ga mu a nan inda aka tsara, kuma inda yake zama cibiyar kasuwancin Kaduna cikin gaggawa. Titin Prince Edward, tuni ya xauki sabon salonsa a yayin da kyawawan gine-gine na zamani na miqewa xaya bayan xaya wasu manya, wasu kuma qanana, amma dukkansu an tsara su ta yadda za su

[1] Stephen A. Amune (ed), *Work and Worship*, Gaskiya Corporation Limited Zaria, 1986, shafi na 44

biya buqatunsu, kowanne xayansu yana bayar da tasa gudunmawa ga arziqin babban birninmu, da lardin da kuma qasa baki xaya. Duk wani sabon ofis, duk wani sabon kamfani, na qara nuna cewa ga dukkan alamar wasu kamfanonin iri daban-daban za su bayyana. Duk wani abin da zai bunqasa harkar safara, wannan muhimmin al'amari a harkar tattalin arziqi, lallai a ba shi goyon baya. Sai a yanzu ne, da aka yi babban titin zuwa Kaciya da na Keffi wanda zai zo ba da daxewa ba, da kuma na Mando wanda bai yi shekaru da yawa ba, za a iya cewa Kaduna ta fara zama mahaxar sufurin qasa. Ina mai farin ciki cewa damar da wannan ya kawo ta fuskar kasuwanci ba a bar ta ta wuce ba.

Kamfanin J. Allen, ba baqo ne ba a cikinmu. Da dama daga cikinmu har yanzu muna kiran sa da sunan Joe Allen, sunansa a shekara sha-biyar zuwa talatin da suka wuce. Abin ban mamaki xan kamfanin nan Allen ya girma. Jarinsa a Nijeriya ya ruvanya sau ashirin a Nijeriya a cikin shekara sha biyu. Muna so mu ga tsohon abokinmu ya qara albarka kuma muna murna cewa sun yi amanna da cewa gabanmu za ta yi kyau, ta yadda suke zuba jari a qasar, ta yin gine-gine da zuba kayan aiki. Wasu abubuwan da suka amfana da su ta fuskar qere-qere da qwarewar kasuwanci, muna fata za ku koya wa matasanmu na Arewa wannan qwarewa, waxanda shugaban kamfanin ya lura akwai buqatar yin haka, matasa masu zamma, da qoqarin su kyautata rayuwarsu da kuma matsayinsu. Allah Ya ba ka nasarar taimakawa wajen kyautata matsayinsu-matsayinsu a wajen aiki mai kyau, da qwarewa, da kuma iya xaukar nauyi.

Shugaba ina taya kamfaninka murna a kan wannan qoqari da ya nuna, ina kuma mai matuqar farin cikin buxe waxannan gine-gine.

Arewa ta taso ci gaban qasaita da halin girma, ta kuma taka rawar gani a duk harkokin da suka shafi kafa sabuwar Nijeriya. Ita ce akan gaba wajen harkar mulki, da sana'a da kasuwanci. Saboda bajintar jama'arta da qwarewa tare da sadaukar da kan shugabaninta, sun haxu sun maida Arewa abar misali, a Nijeriya da qetare. Idan jama'ar wannan jiha suka riqe aqidar Aiki da Ibada wadda Firimiya ya tsaya tsayin daka don ganin ta yi tasiri a kansu, to, babu shakka za su buwaye a duniya. Da wannan nufi ne yana kuma alfahari ya tafi wajen NUNIN Kaduna, inda ya yi jawabi.

Al'ummar da bata cika son gwani ba kan ce, "Yabon Gwani ya zama tilas. "Alhaji Isa Kaita, Wazirin Katsina, K.B.E, C.O.N., wanda yake yana xaya daga cikin manyan Ministocinsa ya ba da shaidar cewa:

"Sardauna na da qwazon yiwa jama'a aiki mai ban mamaki. Baya gajiya wajen tafiye-tafiye ta qasa to jirgin sama don aiwatar da ayyukan jama'a. A cikin jawabansa akwai inda ya ce: "Na sadaukar da kai na gaba xaya don yin aiki tuquru saboda ci gaba da jin daxin mutanen sabuwar Arewa. Na rantse da Allah, ko yau na mutu ba zan bar komai ba sai fa gadon gwagwarmayar neman yanci da jin daxi da mutumcin talakawan wannan qasa."[1]

Kowa ya shaida Sardauna ya cika waxannan al'qawurra da ya xauka: Ya sadaukar da kansa kacokan, ya kuma yi ayyukan da har qasa ta naxe ba za a manta da shi ba. Da kuma ya yi shahada bai bar komai ba, sai ayyukansa da halayensu waxanda suka zamo abun koyi ga na baya. Saboda ai gaba ta wuce baya adda saura! Saboda ya yiwa 'yan zamaninsa zarra, ya sa 'yan wannan zamani ke ma laqabi da cewa, "Sardauna ne Gausul Mulki!"

Firimiya ya cika alqawarin da ya yi a Majalisar Wakilai a lokacin zartar da dokar vulguce Kaduna daga Zariya, a inda ya ce zai yi mata ayyukan da za su dace da matsayinta na Yankin Hedkwata wato *Capital Territory*. Ya kuma yi waxannan ayyukan.

Abubuwan da Sardauna ya yi wa garin Kaduna, wannan littafi ba zai xauke su ba, ban da abubuwan da ya yi waxanda aka ba da tarihinsu, akwai wasu muhimmai wanda wannan gwarzon Kaduna ya yi ko kuma ya taimaka da yinsu. Sauran waxannan wurare kuwa su ne; kafa Babban Kamfanin nan NNDC (Gidan Ahmed Talib) da Bankin Arewa wato, *Bank of the North* da *Defence Industrial Corporation* (DIC), da *Nigerian Defence Academy*, NDA), da *Nigerian Air Force Base* da ke Kaduna da sauransu.

A farkon shekarar 1960 Kwalejin Horasda Sojoji wato *Military Training College* an bunqasa ta don ta zama irin mashahuriyar makarantar horon sojoji ta Ingila da ke Sandhurst. Ita wannan makaranta, Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa, Firayim Ministan Nijeriya ne ya buxe ta. An kafa wannan makarantar na tsawon lokaci akan tudu da ke Arewa da qauyen Abakwa da ke Kaduna. An kuma kafata ne don ta ba da horo ga xaliban sojoji "Cadets" don su sa mu shiga mashahuriyar makarantar soja ta Ingila wato *Royal Military Academy* da ke Sandhurst a Ingila.

Ita wannan makaranta ta bunqasa sosai har ta zama *Nigerian Defence Academy* ta na kuma da matsayin jami'a. Ita ce Jami'ar farko a garin Kaduna. Jami'ar Jihar Kaduna ita ce ta biyu. Akwai kuma sauran jami'o'i masu zaman kan su da ke qoqarin vullowa a wannan gari.

Don zaman lafiyar qasa da jama'arta ya zama tilas a horosda 'yan Sanda da sojoji, a wannan fage ma ba a bar Kaduna a baya ba. Da wannan gari yaci gaba da

---

[1] Stephen A. Amune, *Work and Worship*, shafi na II

bunqasa, sai aka buxe wuraren horasda 'yan Sanda. An kafa wajen horasda 'yan Sanda na farko, a shekarar 1917 wato *Police Depot*. Amma kafa makarantar 'yan Sanda ta Arewa wato Northern Police College ta maye gurbinta. Wannan makaranta ta taimaka sosai wajen bunqasar garin da tabbatar da zaman lafiya.

Ita ma shahararriyar makarantar Kimiya da Fasaha wato *Kaduna Polytechnic* ta dade ta na yaye xalibai waxanda su ka yi fice a fannoni daban-daban. Ita wannan makaranta wacce Sardauna ya kafa ta kai matsayin tafiya kafaxa-da kafaxa da wasu jami'o'i a Nijeriya. Idan samarinmu da 'Yammatanmu suka samu horo mai qyau da qwarewa a sana'o'i daban-daban, to, babu shakka al'umma za ta ci gaba.

Wajen gine-ginen gidajen jama'a, gidajen da Gamji ya gina a Unguwar Turawa sun fi na Gwamna Lugga yawa. Irin gidajen Gamji ana gina su domin su dace da magidanta masu kulle. A yanzu haka a cikin Unguwar Turawa akwai gine-gine irin na Gamji da irin na Lugga waxanda duk sun taimaka sosai wajen qayatar da garin Kaduna. Ministan Ayyuka na wannan lokaci, Alhaji Isa Kaita Wazirin Katsina ya taimaka sosai wajen qayatar da wannan gari.

Ban da qayata garin Kaduna da Gamji ya yi, ya taimaka sosai wajen gina jama'ar garin ta fannin ilimin fasaha da na sana'a. An bai wa jama'a masu yawa da aikin gwamnati ya kawo su Kaduna iznin qaro ilimi ko fahimtar sana'a a qasashen waje a xan qaramin zamaninsa.

Saboda abubuwan da Gamji ya yi wa Kaduna da mazauna cikinta, sun taimaka wajen bunqasar ilimi da addini da sana'a da annashuwa, su ne kuma ginshiqan ci gaban Arewa baki xayanta, don haka sai yaci garin Lugga. Idan mutum ya dubi abubuwan da Gamji ya yi waxanda za a tuna da shi wato *Sardauna's Monuments* da abubuwan da Lugga ya yi wato, *Lugard's Monuments* sai a ga babu shakka abubuwan Gamji sun rinjayi na Lugga, nesa ba kusa ba don haka sai laqabin Kaduna ya canja daga "Kaduna garin Gwamna" zuwa"Kaduna Garin Gamji Xan Qwarai."

Wannan sabon laqabin Kaduna ba an butulcewa Gwamna Lugga ba ne, a'a wannan hikimar masu zance ce ta fito da mutumin da ya yi abin ku-zo-ku-gani. Gamji ya yi wa garin Lugga abin da mahaifin kakarsa, Sarkin Kano Dabo ya yi wa Birnin Kano, wato shi ma yaci garin Lugga, Kaduna kuma ta zama ta Gamji ci-gari, ci garin wani-ba-na-ka ba! Shi ma haka Dabo mahaifin kakar Gamji yaci jalla-babbar Hausa, Kano ta Dabo ci-gari. Nasarorin da Sardauna ya samu a lokacin rayuwarsa sai suka zama muhimmai suka kuma fitar da Arewa daga cikin duhu, suka kuma kai ta tudun natsira. Waxannan ayyuka sai suka zama gagara-koyo don haka ne ma ake masa kirari da "Har qasa ta naxe a na tuna ka."

Sir Ahmadu Bello, shugaba ne mai adalci wanda kowa ya amfana matuqar gaske da mulkinsa. Saboda shi mutum ne mai jinqai da taksayi don haka ne

gwamnatinsa ba ta bar naqasassu a baya ba. A lokacinsa ne aka kafa Marantar Makafi wadda itace ta farko a Afirka ta Yamma.

Makarantar Makafi

gwamnan Jihar Arewa, Sir Bryan Sharwood Smith ne ya buxe wannan muhimmiyar makaranta a watan Agusta na shekarar 1954. Mai girma Shehun Barno, M. Umar Ibn Muhammad El-Kanemi tare da Mai girma Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayero suka buxe ta. A lokacin da yake bikin buxe wannan makaranta Mr. C.R Niven ya ce Jihar Arewa na da makafi masu yawan dubu xari biyu (200,000) wanda ya kai yawan mutanen Ikko, Hedkwatar Nijeriya. Wannan Makaranta ita ce irin ta ta farko a Afirka ta Yamma.

A Kaduna an kafa Makarantar Koya wa Makafi sana'a saboda su ma su amfana da albarkar Aiki da Ibada. Ita wannan Makaranta ba ta En'e ba ce, ba kuma ta gwamnati bace. Makaranta ce da ke zaman kanta. An gina ta ne daga taimakon da ta ke samu daga En'e – En'e da kuma sauran hanyoyi.

Mr. Eric Chapman shi ne shugaban Makarantar wanda ya xebe shekara ashirin na qwarewa a wannan aiki na koyar da Makafi sana'a. A cikin watan Agustan shekarar 1954, aka fara xaukar almajirai na farko. A kuma watan Maris na shekarar 1955 Gwamna ya yi bikin buxe wannan Makaranta inda Sarakuna, Ministoci da manyan baqi suka halarta. An buxe wannan makaranta da xalibai goma sha-biyar. Amma kafin shekara ta zagayo har yawan xaliban yakai hamsin. A dalilin haka ne aka faxaxa makarantar da gine-gine.[1]

A watan Satumban shekarar 1954, Sarakuna suka ziyarci Makarantar koyawa makafi sana'a. Sardaunan Sakkwato, Ministan En'e da kyautata zaman jama'a kuma shugaban Jam'iyyar Taimakon Makafi na Jihar Arewa ya tafi tare da su. Sir Abubakar kuma babban shugaban Jam'iyyar, yana cikin Sarakunan da suka ziyarci wannan Makaranta. A wannan ziyarar ce suka gane wa idanuwansu yadda xalibai ke koyo suna saqar tabarmi da kwanduna. Har ya nuna farin cikinsa da ganin hikimar waxannan xaliban da kuma yadda suka himmatu wajen aikinsu.

Shi kuwa Sardauna sai ya bayyana wa Sarakuna cewa an yi niyyar shagalin buxe Makarantar cikin watan Maris na shekara mai zuwa wato shekarar 1955. A lokacin wannan muhimmiyar ziyara ne sai Mr. E. Chapman, shugaban Makarantar ya zagaya da manyan baqi don suga wannan Makaranta da ci gaban da tayi. Ya kuma bayyanawa Sarakuna irin abubuwan da ake koyarwa, da waxanda ake da niyyar yi a nan gaba.

A lokacin wannan ziyara ta Sarakuna, wannan Makaranta nada makafi goma sha-biyar da ke zaune a kamfawul, da masu koyarwa mutum biyar, sa'an nan masu koyo da dama za su iso ba da daxewa ba. Manufar Jam'iyyar Taimakon

[1] GTK, 28/8/1956

Makafi, ita ce a kowane lardi a kafa wakshof, inda waxanda suka koya a Kaduna za su yi aiki. Ta wannan hanya za su sami abin zaman duniya a bisa qarqashin masu koya sana'a da ke gani, waxanda a yanzu su ke koyo.[1]

An buxe qananan cibiyoyin wakashof na koyon sana'a a wasu lardunan Jihar Arewa, wato *Provincial Blind Workshop* inda ake koya wa makafi sana'o'i daban-daban. A shekarar 1959, Mai girma Firimiya ya ziyarci irin wannan cibiya ta lardin Zariya. A wannan ziyara ce yaga yadda makafi ke koyon xinki. Babban Razdan na Zariya Mr. C. J. L. Reynolds ne ya raka shi. Dukkansu sun yi farin ciki da yadda suka ga makafi na samun horo kamar yadda ya kamace su. gwamnatin Jiha, ta duqufa sosai wajen ganin makafi a Arewa waxanda yawansu ya kai dubu ashirin a wancan zamanin suna samun kulawa da horo da suka kamace su.

Irin wannan aiki na kulawa da miskinai da naqasassu, ya samu kyakkawan tushe, ya kuma zama abin nuna misali a wannan zamani. Haka kuma irin wannan aiki yayi kyakkawan tasiri domin har yanzu naqasassun da suka amfana da irin wannan shirin, suna yiwa Sardauna da 'yan Majalisarsa addu'o'in alheri a kullum, musamman a wannnan lokaci da ba a damu da su ba. Don haka ne Sarkin Kutaren Sabon Garin Zariya, Malam Sulaiman ya koka da cewa: " Rabon mu da gwamnati tun Zamanin Sardauna."[2]

Ya yi wannan furuci ne saboda yana xaya daga cikin naqasassun da suka amfana da ayyukan gwamnatin Firimiya. Sarkin Kutaren, ya bayyana cewa tsawon shekaru arba'in kutaren Sabon Garin Zariya da sauran na Jihar Kaduna ba su samu fa'ida daga gwamnati ba, ya ci gaba da cewa, baya ga qwayoyin maganin cutar kuturta, da qungiyoyin bada tallafi na qasashen waje ke bayarwa, kutare a yankinsu basu sami wani tallafi daga hukuma ba. Ya kuma ce mafi yawan kutaren yankin sun dogara ne ga sadakar da ake basu don tafiyar da rayuwarsu.[3]

Ayya! Albasa bata yi halin ruwa ba, da an ci gaba da shirin da gwamnatin Firimiya ta kafa na kula da miskinai da naqasassu da miliyoyin waxannan bayin rayuwa ba. Domin kuwa da mafi yawa daga cikin su un sami wajen dogaro da kansu ba yawan barace-barace ba. An ce tuna baya shi ne roqo. Don haka ne Sarkin Kutaren ya tuna da Zamanin Sardauna, inda ya ce:

"Na yi shekaru 75 yanzu amma lokacin da nike iya tunawa da cewa munga tasirin Gwamnatoci, shi ne zamanin mulkin Sardaunan Sakkwato. Saboda ya riqa ziyartammu a Cibiyar Kula da Lafiyar Kutare da Ciwon Tarin Fuka ta Zariya (National Leprosy and Tuberclosis Center Zariya). Ya kuma riqa gamuwa

---

1 GTK, 22/9/1954, shafi na 8

2 Jaridar Aminiya, Juma'a 18 ga Disamba, 2009, shafi na 29.

3 *Ibid*.

da mu, inda ya riqa zagawa yana gaisawa da mu xaya bayan xaya. Ya kuma riqa gamuwa da mu, inda ya riqa tambayar halim da mu ke ciki. Sannan ya rarraba mana wasu takardu a sa'ad da al'amarin ya faru ina nan tare da matata a wurin.

Ya bada umarnin cewa a riqa bamu magunguna kyauta. Kafin ya bar wurin sai da ya raba mana kyautar kuxi. Bayan Sardauna, akwai wani Shugaban Qasar Soja da ya kawo mana ziyara tare da matarsa. Shi ya karvi mulki daga hannun Buhari (Janar Babangida Mai Ritaya). Aka tara mu a wuri xaya, amma har ya zo ya tafi, mu bamu san ko wane ne ba. A lokacin, yana zagaye da sojoji uku da makamai, kuma har ya tafi, bai bamu komai ba. Har yanzu babu shugaban Qaramar Hukuma ko Gwamna da ya ziyarce mu, bayan ziyarar Sardauna."[1]

Babu shakka, gwmnatin Sardaunba ta nuna tausayi, da jinqai wajen kula da naqasassu ta hanya mafi dacewa wato ta koya musu sana'o'i don su dogara da kansu. Kamar yadda kowa ya sani, waxannan bayin Allah suna da 'ya'ya da jikoki waxanda basu naqasa ba kuma sun cancanci zuwa makaranta, amma abin takaici, shi ne sai su rasa wannnan dama saboda naqasar iyaye da kakannin su. Bugu da qari ma, matan waxannan naqasassu, na shan baqar wuya wajen goyon-ciki da shayarwa. A wannan zamani, da duniya ta ci gaba, ai abin takaici ne a ga 'yan Arewa ne suka yi suna wajen barace-barace a qasarsu da qasashen makwautansu har da qetare. Ai lokaci ya yi da za mu nuna wa duniya, mu 'yan Arewa ne na asali waxanda su ke kan gaba wajen taimakon jama'a amma ba mu shagala wajen taimakon kanmu ba.

Sardauna Sir Ahmadu Bello wani qasaitaccen mutum ne, wanda ya farkar da jama'a a lokacin da maqiya da abokan gaba suka yunquro don su danne ta. Shi ne ya baiwa jama'ar Arewa kyakkyawar manufa da alqibla ta Aiki da Ibada. Sa'an nan ya basu madafa wajen kafa masu masana'antu da kamfanoni. Kaico! Sai garma ta karye da sauran aiki!

Alhaji Isa Kaita, Wazirin Katsina ne ya ce ranar Lahadi 17 ga Janairu na shekarar 1966, Manjo Nzeogwu ya shaida masa kai tsaye da cewa, "mun kashe Sardauna ne saboda shirinsa na "Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa." Saboda haka an kashe shi ne ba don zalunci ba amma domin aiwatar da adalci a gwagwarmayarsa ta baiwa mai haqqi, haqqinsa. Mai kaya ya mallaki kayansa. Babu wani abin da ya tayar wa 'yan Kudu rai ya kuma hasala su kamar aiwatar da Ba 'Yan Arewa Jan Ragamar Arewa, wato *Northernization Policy* da Firimiya ya yi. A dalilin haka ne aka kifar da gwamnatinsa aka kuma halaka shi. Don kuwa har yanzu 'yan Kudu sun xauki cewar ai Arewa akushin tuwonsu ce ta gado, 'ya'ya da jikoki abadan!

---

[1] Jaridar Aminiya, Juma'a 18 ga Disamba, 2009, shafi na 29.

KASHI NA GOMA SHA-BIYU

Ba 'Yan Arewa Jan Arewa

Sukurkucewar Al'amari

Idan aka bi qwaqqwafin dalilan da suka sa Arewa ke dushewa a kusan duk harkokin ci gaba a Nijeriya a yanzu, za a ga sun samo tushe ne daga irin ilimi da horo da Turawa suka baiwa 'Yan Arewa tun farko. Saboda illar mulki takan Sarakunansu, irin ilimi ne da horo da amfanin su ba su wuce Arewa ba. Saboda ba su da amfanin komai in sun qetare Kogin Kwara don ilimi ne da horon aiki da suke kamar, gani-na-yika. Amma ba Turawan mulki kawai ke da laifi ba, har ma 'Yan Arewa masu ilimi na wannan zamani ba su taimaka wajen inganta bayar da ilimi tare da faxaxa shi, da kuma sauqaqa samun sa ba. Ya kamata ayi bayani sosai akan *Colonial Education* da mumman tasirin sa a kan 'Yan Arewa. Domin shi ne maqasudin sukurkucewar al'amari a Jihar Arewa.

Haka zalika, an yi nuni da cewa masu ilimin wancan zamani sun bar kaza cikin gashinta ne, saboda ko da yake sun fahimci Turawa na yaudarar 'Yan Arewa wajen ba da ilimi, amma ba su tavuka komai ba wajen maganin wannan mummunan al'amari wanda ya yi mummunan tasiri a kan jama'arsu ba. Abin da qalilan daga cikin masu ilimi, a wancan zamani suka yi bai wuce kwaqwazo a dandalin siyasa ko rubuce-rubucen waqoqi masu tayar da hankali ba. Ba a samu wani gwarzo da ya fito ya qalubalanci tsarin bayar da ilimin boko don yalwata shi da faxaxa shi ba. Domin da an sami damar yin haka tun a shekarar 1930, da Arewa ta taso da isassun masu ilimi da ma'aikata dai-dai gwargwado. Yadda Turawa suka shirya haka suka zartar har ya zuwa shekarar 1940, wato sai da Turawa suka sami shekaru talatin suna yaudarar 'Yan Arewa da sunan ba su ilimi da horar da ma'aikata. Abin da ya kamata a yi na farko shi ne a jagoranci "Ba 'Yan Arewa ilimi mai zurfi kuma mai sauqi." A rashin yin haka ne 'Yan Arewa suka gaza matuqar gaske waje samar da isassun ma'aikata.

A maimakon a fahimci gazawar Arewa, ta ainihi, wato suna da naqasu wajen ilimin da aka shekara talatin ana cunkusa masu, sai abin takaici aka koma hangen 'Yan Kudu. A wata fafitikar cike tazarar ilimi da wannan yanki wanda har yanzu ya faskara! A dalilin haka sai aka shiga kwaqwazon tazarar ilimi a tsakanin Arewa da Kudu da kuma hanyoyin da za a bi a cike wannan babban givi. To, ya kamata waxanda ake cutar da su, suka kuma gane ana cutar da su, amma kuma suka kasa yin komai, su ne za su iya cike wani makeken givin ilimi da ke akwai a tsakanin Kudu da Arewa? Abin da za a ce shi ne cakulkuli ake wa sha'anin ilimi domin a kau da hankalin jama'a daga ganin gazawar masu ilimin zamani tun farko har yanzu.

Bugu da qari, ba cike tazarar ilimi Arewa ke buqata ba, abin da take buqata shi ne ta tsaya da qafafunta a duk harkokin rayuwa ba tare da ta dogara ga 'Yan Kudu ko 'Yan qetare ba. To, hakan ba zai yiwu ba, sai an faxaxa ilimi an kuma sauqaqa ba da shi ga kowa. Wannan fa shi masu ilimi ke qin yi tun farko har ya zuwa yanzu. A maimakon haka sai aka shiga wasan kura da harkar ilimi a Arewa. Alal misali, ana iya nuni da ci gaban 'Yan Kudu da kuma kururuta cewar ga 'yan Kudu nan tafe za su danne 'yan Arewa. A duk tsawon lokacin da ake wannan vavatun 'Yan Arewa ba su da masu ilimi da yawa suna kuma da qarancin ma'aikata. Saboda haka sai nuni da waxannan matsaloli, ya share fagen xaukar wata sabuwar gwagwarmaya. Ita wannan gwagwarmayar ta samu karvuwa ga 'Yan Arewa, an kuma daxe ana kururuta wannan sabon yaqi da shugabannin Arewa suka xauka wanda ya sa gwamnan Arewa, Sir, Bryan ya yi tsokaci akan wannan batu inda ya ce:

"Xaya daga cikin abubuwan da na ga Ministocin Arewa, duk da kangadonsu, suka qi kangado, shi ne wurin yaqin da suka buxe, baki buxe, ido rufe, kunne rufe, wurin baiwa 'yan Arewa jagorancin Arewa. Sun yi imani a rayukansu cewa tatsar da mutanen Kudu su ke yi wa Arewa ta isa haka nan. Tura ta kai bango! In ka yi musu magana, suka kawo maka dalilansu, da misalai masu yawa a kan haka, dole ka bisu a hankali. Ba wata shawara da za kawo musu ta wai a sake hanyar da suka xauka ta baiwa 'yan Arewa jagorancin Arewa."[1]

Wata qila Gwamna ya ga rashin kangado Arewa ta yi wajen wannan maganar ta Mulkin Arewa sai Xan Arewa a maimakon gina Arewa akan ilimi mai zurfi. Saboda da ilimi sauqaqqe kuma mai zurfi ne za a samu isassun ma'aikatan da za su xauki ragamar jagorancin Arewa. Haka-zalika duk wanda ya san cewa al'umma ba za ta ginu ta yi qarfi, ta bunqasa, har ta riqa tafiya kafaxa da kafaxa da sauron al'ummomi ba, sai ta sha gwargwarmaya iri-iri, ta faxi ta tashi kafin ta kai inda za ta tsaya da qafafunta dimir dimir. Rashin kangado ne a xauki matakan kare ta daga wahalhalun rayuwa da suke wajibi. A saboda haka ne wataqila, Mai Wandon Qarfe ya yi qorafin cewa Ministocin Arewa sun shiga yaqi baki buxe, ido rufe kuma kunne rufe. Wato ba sa ji ba sa gani ballantana a ba su shawara su ganta su xauka. Idan kuwa suna ji suna kuma gani da yaqin ba xan Arewa ilimi mai zurfi mai kuma sauqi suka xauka. Kamar yadda al'amuran Arewa suka sukurkuce saboda Mulkin Mallaka, ai babu maganin da yafi baiwa kowane xan Arewa ilimi sahihi. Matsalar farko da wannan shiri ya fuskan ta shi ne qarancin ilimi a Arewa.

Idan yanzu mu ka dubi yadda Arewa ta sheqa a guje wajen Mulkin Kai da samun 'yanci, da kuma yadda aka xauki gwagwarmayar "Ba 'Yan Arewa

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 71

Jagorancin Arewa', da kuma abubuwan da suka biyo baya, mu na iya cewa Sardauna bai cimma muradinsa ba saboda an yi kitso da qwarqwata ne. Wannan itace matsalar wannan shiri na biyu gaskiya ai sunanta gaskiya. Maqasudin xaukar wannan qasaitaccen shiri, kamar yadda Sir Bryan ya ce ne shugabannin Arewa sun yi imani a rayukansu cewa tatsar da mutanen Kudu su ke yi wa Arewa ya isa haka nan. Don gudun wannan tatsar, sai a baiwa 'Yan Arewa jan ragarmar Jiharsu, a bisa kyakkyawan zaton ba za su ci amanar da aka xanka masu ba, ballanta na su tatsi Jiharsu Arewa, ko su yi mata zagon qasa don wasu su samu galabar tatsar ta.

Ashe an yi gudun gara ne aka faxa zago! Don kuwa tun kafin a kawo ga wannan lokaci, an kasafta Arewa zuwa azuzuwa daban-daban takan ilimin boko, suna kuma hamayya da juna. Akan wannan tsari ne aka xora ginin sabuwar Arewa. Da aka ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, sai 'yan Arewa masara qarfi suka faxa hannun 'yan azuzuwa masu qarfi kuma 'yan tsiraru. Da samun wannan ragamar jagorancin Arewa, sai suka danne sauran azuzuwan jama'a masu yawa marasa qarfi. Wannan shi ne illa na farko kuma mai munin gaske. Ta *Colonial Education* aka baiwa Arewa ilimi kuqumi kuma gurguntacce. Saboda haka sai ya qeqashe ya zama wani babban tarnaqin da ya hana Arewa ci gaba. Ta hanyar bada wannan ilimin ne aka rarraba jama'a zuwa azuzuwa wanda shi ma ya qeqashe ya zama kutingwilar hana Arewa ci gaba. Saboda haka da baqin zare aka fara saqar hanyar gina sabuwar Arewa. Ta hanyar bada ilimi sai aka faxa haxarin rarraba jama'a sashi-sashi masu hamayya da juna. Alhaji Dr. Abubakar Imam ya aibanta *Indirect Rule* saboda rarraba jama'ar Arewa zuwa gidaje uku: Sarakuna ko masu mulki, da Ma'aikata da talakawa. Amma *Colonial Education* ne ya vata rufin Jajimanci ya maida Almajiri qasqantacce marsa galihu a qasarsa ta haihuwa saboda rashin ilimin boko. Ta hanyar bada *Colonial Education* ne aka cimma nasarar kasafta al'ummar Arewa zuwa ajujuwa daban-daban masu kuma gasa da hamayya da juna, wato Samfurin *Hindu Caste System* aka dasa a Arewa. Wannan tsari ake bi har yanzu. Shi ne kuma ake kira tsarin Jajmananci. Saboda haka wannan tsarin Jajmananci da ya kafa Arewa shi ne ya maida Almajirai "Untouchables".

A kan wannan tsari ne qeqasasshe aka gina shirin ba 'yan Arewa jagorancin Arewa. Don haka ne aka ce an yi kitso da qwarqwata. Sabdoa wannan shiri zai haifar da wani sashe mai qarfi ya danne wani sashe mara qarfi a gwagwarmayar neman wanzuwa. A dalilin haka ne shugabannin mulki 'yan Siyasa da sojoji sai suka sami ragamar jagorancin Arewa gaba xayanta, Sarakuna kuma aka koma da su bayan fage. A qarshen al'amari sai aka wayi gari kuma wasu 'yan Arewa don son kuxi ko mulki sai suka sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Kudu. Don haka ne a sabuwar Arewa aka wayi gari wani sashe ya danne wani sashen wannan al'umma. Abin takaici shi ne sai tatsar 'yan Arewa kan 'Yan Arewa ta maye gurbin

tatsan mutanen Kudu. Wannan danniyar wani sashen 'Yan Arewa a kan wani sashe, ya fi danniyar mutanen Kudu muni da illoli masu yawa, saboda wasu dalilai masu dama.

A qasar Hindu ta haihuwa ne wani tsatso ke fin wani tsatso ba domin komai ba sai don darajar nasabarsa. A Arewa kuwa ta ilimin boko ne wani tsatso ke fin wani tsatso saboda a samun bambancin darajar nasaba ba domin ba sai don ilimin boko. Saboda haka, da Indiya da Arewacin Nijeriya duk *Hindu Caste System* suke bi. Koda yake Arewa a fakaice ta ke bin tsarin Jajmananci, shi ne kuma ya maida ita fifa'iya koma baya a harkokin jama'ar Nijeriya. A dalilin Arewa na bin tsarin Jajmananci ne sai shirin Ba 'Yan Arewa Jan Ragamar Arewa wato *Northernisation Policy* ya zama tarnaqin hana ta ci gaba. Saboda an yi kitso ne da qwarqwata!

Kitso da Qwarqwata

Akasarin waxanda suka fito makaranta a wancan lokaci, sun fito ne da yunwarsu yi mulki, wani buri da qungiyar *College Old Boys Association* ta assasa masu. Saboda haka suke neman damar da za su karvi mulki daga Sarakuna, abin da 'Yan Kwaleji su ke kira Qwatar Girma, da iqirarin kare Arewa daga mallakar mutanen Kudu, wannan gwagwarmayar suka kira Qwatar 'Yanci. Bari in qara nanatawa da cewa, to, mai zai hana waxanda suke da waxannan qalubale a gabansu, qara faxaxa ilimi da sauqaqa shi don a samu isassun masu ilimi da ma'aikata don cimma waxannan manufofi? Abin takaici sai suka duqufa wajen gwagwarmayar "Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa, suka kuma kururunta wannan shiri, duk da sun san ba su da isassun masu ilimi da za a ba ragamar jagorancin Arewa.

Ana cikin qoqarin aiwatar da wannan shiri, sai matsalar ta yi harshen damo. Matsalar Ba 'Yan Nijeriya Jan Ragamar Nijeriya ta hudo kai. Qaqa-tsara-qaqa! Wanne ne ba wanne ne ba, idan aka ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, a guraben ayyukan gwamnati a jiha, ina za a samu waxanda za su ci ke guraben ma'aikata a Federa, wato qasa baki xaya? Saboda haka hangen wannan babbar matsalar ne wataqila, Sir Bryan ya cewa shubannanin Arewa, "duk da kangadonsu, suka qi kangado."

Akwai abubuwa biyu da 'yan Kwaleji suke fitowa da su daga makarantunsu: qin Sarakuna da qin faxaxa ilimin boko. Dalilin da ya sa suke qin Sarakuna shi ne don suna hamayya da muxlaqin mulkinsu ne wanda suke so su rusa domin su qwato wa kansu girma, amma ba Arewa ba. Suna kuma qin faxaxa ilimin boko ne, saboda su yi mulkin 'Yan tsiraru, masu qarfi, waxanda za su riqe komai a hannunsu wato su kafa muxlaqin mulki na dundundun. Domin haka ne "suka buxe baki, ido rufe, kunne rufe, wurin baiwa 'Yan Arewa Jagorancin Arewa", inji Mai Wandon Qarfe. Wannan gwagwarmayar ce ta fifita son mulki fiye da ilimi a

zukatan 'yan Makaranta a Arewa. An daxe ba abin da xaliban Arewa ke son karantawa a manyan makarantu sai fannin ilimi mulkin jama'a wato *Public Administration* da fannin siyasa wato *Political Science*. Domin su fito daga makarantu cikin shirin karvar ragamar mulki a wani vangare na Arewa: Saboda haka suka yi watsi da aikin gona da sana'a. Ilimin Kimiyya kuma suka yi masa xaukar sakainar kashi. A dalilin haka sai muce sun nuna rashin kangadon. Ana iya cewa ma masu ilimi a Arewa, a Siyasar Farko sun taimaka wajen gazawa 'yan bokon wannan zamani, saboda rashin kafa kyakkyawan harsashin ilimi mai faxi. Har yanzu ana tauye yaxuwar ilimi ne don mulkin 'Yan tsiraru ya yi qarfi ya kuma buwaya. Irin mulkin da ya haifar da wani sashen al'umma mai qarfi ya danne mai yawa mara qarfi.

Ko da yake Turawa sun taimaka gaya wajen ba 'yan Arewa gurguntaccen ilimi amma duk da haka ba ayi wani hovvasa wajen shawo kan wannan matsala ba saboda wata manufar 'yan tsiraru masu wannan ilimi. Da wuya a gane irin wannan danniyar cin amana, saboda waxanda suke danniyar ba su bambanta da waxanda suka danne ba, ta wajen zama ko addini ko qabila da al'ada. Haka zalika, da wuya a xauki matakin gwagwarmayan qwatar yanci daga irin wannan muxlaqin Mulkin Mallaka. Don haka danniya ce dauwamammiya sai inda maslaha ta tsaya. Da aka vallo a guje, wajen gudun gara sai aka faxa zago, ai ba a yi sa'a ba, da danqa jagorancin Arewa a hannun wasu tsiraru da suke da aqidar cewa ilimin boko, nasu ne da 'ya'yansu. Saboda su ne ke cin garavasar tsarin Jajmananci da Arewa ke bi sakaka. Kuma ilimin boko shi ne makamin riqe ragamar mulki saboda haka sai suka daqile ci gaban ilimi don su dauwama a mulkin jama'arsu. Wato dai an yi kitso da qwarqwata ke nan.

Don gudun kada Arewa ta sha wuya, da aquba daga tatsar 'yan Kudu sai ta faxa wani mawuyacin hali, wanda yake da qyar ta sami mafita. Wato tatsar 'yan Arewa daga 'yan Arewa! Rayuwar al'umma kamar rayuwar jariri ce har ya zuwa girmansa, ya zama mutum balagagge kuma mai hankali. A lokacin yana jariri zai yi ta qoqarin iya zama. A wannan lokaci sai ya zauna ya faxi ya kuma tsala kuka saboda zafin da ya ji wajen faxuwa. A hankali sai ka ganshi shi yana rarrafe daga nan sai ya koyi tsayawa. Idan ya iya tsayuwa, sai ya fara koyan tafiya yana ta-ta-ta. Haka kuma a wannan lokaci zai riqa faxuwa yana tashi har ya iya tafiya. Wajen iya tafiya da gudu ya kan faxi ya yi rauni. Ana haka wata rana sai ka ganshi ya girma ya zama mutum. Idan saboda son da iyayensa ke yi masa, suka ji tsoron zai citu wajen koyon dabo ko tafiya, suka hana shi, to, son su zai cutar da shi. Abin da iyaye za su yi, sai su sa ido a kansa su na kaffa-kaffa da shi, amma ba su hana shi qoqarin koyon dabo da tafiya ba don gudun kada ya ji rauni ba.

Haka kuma al'umma kamar ya'yan itace take kamar mangwaro, idan ana so su yi kyau da daxi, tilas a barsu ruwa da iska su buge su, rana kuma ta koxa su. A cikin wannan mawuyacin lokaci suke qosawa, su kuma harba kafin su nuna.

Amma idan aka nika su don su yi saurin nuna, to, kamar yadda kowa ya sani ne, nunan sama ya fi nuko daxi da zaqi, da qyau da qarin lafiya. Idan ana son al'umma ta yi nagarta, to, kada a nuka ta. Ba 'Yan Arewa jagorancin Arewa, wani nuko ne da ya cire wa al'ummarta kishi, qwazo da nagarta. Saboda ya maida su 'yan abamu!

Al'umma tana kama da dabba wajen dogaro da kai, da jure wahal-halu wajen neman abinci, da nuna qarfi da dabara wajen kare kai daga abokan gaba. Alal misali, da beraye su ka dame ni da varna, suna cin ye mani litattafai, sai na kawo xan qaramin mage namiji don in kiwata shi, har ya girma ya zama mazuru, ya kore mani waxannan veraye. Amma sai na zaqe wajen son sa. Saboda kullum sai in riqa ba shi soyayyen kifi yana ci. Saboda haka kafin ka ce me! har ya girma; ya yi mulmul ya zama vuvvukeke. Amma abin takaici maimakon wannan mazuru ya riqa cafke beraye yana ci, sai naga ya shagala wajen kallon verayen da suke fareti a gabansa suna kuma yi mani varna sosai.

Da ganin haka sai hankali na ya tashi har na riqa ba da labarin wannan qawancen Muzuru da Veraye a gidana. Sai aka ce, ai laifina ne da na sangarta wannan muzuru da nake ba shi abinci, domin haka ba zai nemo abincinsa ba. Domin duk wanda ake ba shi ba zai nemi na kansa ba saboda lalaci. Haka kuma ba zai daraja abin da aka ba shi ba. Domin haka sai ci a maho, ya kashe masa qomaji da kuzari wajen nema. Waxannan halaye suke haifar da lalaci da tumasanci da mutuwar zuci. Inda mutuwar zuci ta yi katutu sai tumasanci ya kafu sosai.

Saboda haka idan na ce Ba 'Yan Arewa jagorancin Arewa, ya sangarta su ya kuma cunkusa maso lalaci da mutuwar zuci, ba za a yi mani rina ba. Ko an yi mani, zan daure harbi, ai gaskiya sunanta gaskiya. Don haka zan qara da cewa da 'Yan Kudu ne suka mallake mu, da mun sami wasu shugabannin da za su yi mana jagorar yaqin Qwatar 'Yanci. Da hakan ya faru da mun tashi da kishin qasarmu, da addininmu, da qabilarmu da al'adunmu. Da waxannan halaye sun taimakemu wajen kafa qasa mai buwaya. A maimakon haka ne sai gamu mun maida Arewa saniyar tatsa ga wasu shugabannin Arewa da abokansu mutanen Kudu. Har ya kai yanzu Arewa ba ta da katavus, saboda dogaro da 'Yan Kudu wajen ma'aikatan lafiya, ma'aikatan Tsaro da injiniyoyi da 'Yan Kasuwa. Abin da Ba Yan Arewa Jagorancin Arewa, ya haifar mafi muni, shi ne ya maida Arewa kidahuma. Wanda ba shi ne manufar Firimiya ba. Saboda Mai girma Sardauna Ahmadu ya yi jawabi a rediyon Nijeriya, yana kiran 'yan Arewa su zavi 'yan NPC su wakilce a Majalisar Nijeriya, a shekarar 1954. Ya ce:

"Mu Jam'iyyar NPC mun tabbata babu wanda ya san Arewa fiye da 'yan Arewa, kuma mun tabbata duk irin wahalce – wahalcemmu na Jihar Arewa, babu

wanda zai iya gyara mana su, im ba mu da kammu ba, mutanen Arewa."[1] Daga nan sai Firimiya ya yi gargaxi da cewa: "Mutanen da za ku zava, ya kamata su zama amintattu, mutane irin waxanda don kuxi ko don kwaxayin girma, ba za su sayad da Arewa da jama'arta ga mutanen Kudu ba"[2].

A wannan jawabi Firimiya ya nuna alqibla da muhimmancin shirinsa na "Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa", ya kuma yi nuni da haxarin da ke qunshe wato wasu na iya amfani da wannan damar su sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Kudu don samun kuxi ko don zalamar neman muqami. Firimiya ya yi wannan gargaxi ne saboda gudun kada ya yi kitso da qwarqwata ya baiwa wasu 'yan Arewa mara sa kishin Arewa, jagorancin Arewa. Ayya, ashe qaddara ta riga fata!

Tun kafin a aiwatar da wannan shiri mai kyawon maciji, an daxe ana tafka mahawar a kansa. Jama'a da yawa sun faxi ra'ayinsu a kafaffen watsa labarai na rediyo da jaridu. Alal misali, M. Salihu Kwantagora, a shekarar 1956 ya rubutowa filin faxi-sonka wani ra'ayinsa domin *A Gane Matsalar Arewa A Hannun 'Yan Arewa*, inda ya ce:

> *Zuwa Ga Editor*
>
> *Bayan gaisuwa, ina so ka taimake ni in yi magana a Gaskiya bisa ga muhimmin abin da mutane suka damu da yin maganganu a kansa,"Arewa a hannun 'Yan Arewa." Ina so in jawo hankalin jama'a, su gane wannan matsala ta mawuyacin abu ne. Ni kan sha karanta maganganun mutane daban-daban a kansa, waxansu suna yabawa, waxansu suna kushewa.*
>
> *To, bisa ga haqiqanin gaskiya, kushewa ya fi yabon yawa. Amma ya kamata ga duk mai hankali ya lura da kyau akan abin da yake ya kushe. Kada mutum ya kula da mafi yawan abin da ke sarari ga aiki, in zai yi zargi bisa aikin. Shi kuma mai yabo kada kuskura ya yi yabo har ya zarce kyaun aiki.*
>
> *To, ko da yake na yi wannan bayani ba zan kasa yin zargi ga matsalar ba. Ni ina cikin masu zargin rashin saurin wannan al'amari. Ko da yake ba zan iya cewa ba a kama hanya ba, sai dai in ce an kama doguwar hanya ne ga bin haqqin amsar ragamar Arewa ga 'yan Arewa. Kuma hanya xaya tal a ke bi. Ba zan ce ba a aikata komai ba, sai dai in ce duk abin da aka yi na fuskar yabo, an yi shi ne faxuwa dai-dai zama.*

---

[1] GTK Ta 640, 15/15/1954.

[2] *Ibid.*

Dalilina shi ne har yanzu ni na ga dai hanya xaya tal-tal tukun ake bi, alhali bisa ga zatona akwai hanyoyi da ya kamata a bi. Akwai ximbin jama'a mabambanta da ya kamata a tuttura cikin hanyoyin nan da yake za a sami nasara. Misali a kan yi ta cewa bai kamata a bar mata ba a baya bisa fuskan jagorancin Arewa. Amma me ya auku ga wannan fanni. Matan Arewa a baya su ke qwarai da gaske, fiye da shekara goma a ke ta tura yara mata makarantu, suna fitowa suna kama ayyuka, amma matan Arewa guda nawa ne yau a ke ji a fili? Samun matsayin Siniya Sabis a gwamnati ba shi ne kaxai abin buga qirji da fariya ba.

Har yanzu babu ma'aikatan gwamnati wadda xan Arewa kawai ke wulgayya cikinta, komai qaqanta dai sai an sami xan Kudu liqe ciki. Ban da aikin gwamnati, akwai muhimman sha'anoni a nan qasa da yake 'ya'yan wata qasa sun haye sun yi kane-kane. Ban ga alamar ana gurin xaure wa 'yan qasa gindi su same shi ba. Har yanzu dai son fadanci da zaven kai da nuna mulki a qasar nan bai qaura ba.

Don haka dai sai mu roqi Allah Ya shirye mu Ya fahintar da mu gaskiya ya ba mu ikon yarda da ita, ya fahintar da mu qarya ya nufe mu nisantarta.[1]

A wannan wasiqar za mu fahimci cewa ko a wancan zamani jama'a da yawa basu goyi bayan wannan shiri ba saboda masu kushewa sun fi yawa. Akwai matsaloli da yawa da kan iya hana wannan shiri kai wa ga nasara. Wani babban cikas da shirin ya samu shi ne rashin ma'aikata. Wanda qarancin ilimi ya haifar. Horar da ma'aikata abu ne da zai xauki lokaci qwarai da gaske a lokacin da babu wannan lokaci. Arewa ba ta da isassun masu ilimi da ma'aikata, babu kuma wani katafaren shiri da aka yi don baiwa 'yan Arewa ilimi mai sauqi. A lokacin da ake kwarmaton cike tazarar ilimi tsakanin Arewa da Kudu, a wannan lokaci kuwa kwaleji qwaya xaya rak Arewa ke da shi wadda ita ce kwalejin Katsina. A dalilin tazarar ilimi da Kudu ta baiwa Arewa shi ne yasa suke xaukar 'yan Arewa jahilai waxanda basu isa su ja dasu a harkokin rayuwa ba. Alhaji Abubakar Imam ya ce: "Yan Arewa nada yawan mutane miliyan goma sha-xaya amma abin takaici kwalejinta guda xaya ne rak! A dalilin haka take fidda xalibai goma sha-biyu ko goma sha-biyar zuwa ashirin kuma da qyar a kowace shekara. A Kudu kuwa akwai irin wannan kwaleji da yawan gaske"[2]

---

1 GTK 20 ga Nuwamba, 1956

2 George Amale Kwanashie, *The Making of the North in Nigeria*: 1900-1965, Arewa House Ahmadu Bello University, Press Zaria (Nigeria) shafi na 83-84

Bugu da qari kuma a wannan kwalejin gurguntaccen ilimi aka riqa baiwa 'yan Arewa har na lokaci mai tsawo. Saboda haka ne takardar shaidar fita wannan kwaleji bata da amfani in ta fita daga Arewa. 'Yan Arewa ba su gane Turawa na yaudarar su ba ne sai a shekarar 1940 da suka yi yunqurin zuwa qetare neman qarin ilimi. A wannan lokaci ne aka ce masu ai basu da ilimin da ya dace zuwa qetare. To, abin da ya kamata sai a dunfari matsalar ilimi matuqar gaske don a samu isassun ma'aikata. Da ilimi ake samun, ma'aikata qwararru, amma hankalin jama'a sai ya raja'a wajen neman muqami wato muqamin Siniya Sabis a gwamnati, wani babban matsayi da zai baiwa mutum damar nuna iko da fariya.

Ana fuskantar rashin ilimi, sai aka riqa maganar baiwa mata ilimi da kuma damar su fito su yi aiki. M. Isa Wali ne ya jagoranci wannan shiri wanda bai je ko'ina ba. Ta yin rubuce-rubuce a jaridu. M. Aminu Kano shi ma ya yi koqarin farkadda jama'a akan ilimin mata. Don kuwa kamar yadda na sha nanatawa, abin da Arewa ke nema a wannan lokaci shi ne bayar da ilimin kyauta, ga kowa wani abu da shugabannin ba sa son yi. Ilimin boko tun da ya taso a Arewa, ilimi ne na tsiraru musamman masu hannu da shuni ko masu mulki. Jihar Yamma ta fidda shirin bada ilimin Firamare kyauta a shekarar 1955. Jihar Gabas ta bi sawu a shekarar 1957. Amma Jihar Arewa da take koma-baya-a harkar ilimi sai ta qeqasa-qasa ta qi. To, idan jari hujja ne a Arewa ma ai ilimin boko hujja ne.

Ilimi Hujja

A lokacin da Jihar Arewa ke tasowa domin shiga 'yantacciyar jiha a wannan lokaci ne tsarin jari Hujja ke kankama a qasashen duniya masu Tasowa. Har ila yau a wannan lokaci wani irin bahagon tsari ke tasowa a Arewa wato Ilimi Hujja Addinin musulunci ne ya wajabta neman ilimi akan kowane mutum, mace da namiji, saboda muhimmancinsa a rayuwar xan-Adam.

Sahihin ilimi mai amfani shi ne wanda zai kyautata rayuwar mutum ya kuma ingantata domin cin moriyarta a duniya da lahira. Idan mutum ya samu ilimi sahihi kuma isasshe to, zai fita daga talauci da mulkin danniya. To, abin da Mulkin Mallaka ya haifarwa Arewa shi ne ya kashe ilimin musulunci ya kuma maida ilimin boko "ilimi" Hujja wato kamar yadda "jari" yake Hujja. Saboda haka sai ya zama na 'yan tsiraru waxanda a saboda salon mullaka suke amfani da iliminsu a matsayin hujjarsu ta mallaka jama'arsu. Mulkinsu kuma ya tauye ci gaban al'ummar saboda ilimin su gurguntacce ne, saninsu kuma ququmi ne.

Gwamna Lugga ne ya sagale muhimmancin ilimin Addinin Musulunci ga jama'ar Arewa a shekarar 1903. a lokacin da ya yi zaman farko da shugabannin Daular Usmumaniyya da ya hanvare. A wannan lokacin ne ya ce da su, "Ba ruwan gwamnati da addini." To duk wani da gwamnati ba ruwanta da shi da muhimmanci. Saboda haka ba ruwan gwamnati da duk mai wannan ilimi. Gwamna Lugga ya sagale muhimmancin ilimin Addinin Musulunci ne domin

ilimin boko ya zama hujjar zama xan Arewa wanda Hwamnati ta san da zamansa. Saboda haka ne tun daga wannan lokaci har yanzu Makarantun allo da malamansu suka zama 'yan Borar Arewa. Makarantun boko da masu ilimin zamani kuwa su ne 'yan Mowan gwamnati. Wannan tsari ake bi tun daga shekarar 1903 har yanzu. A dalilin haka ne ake tauye ilimin boko don ya zama hujja babba a zama xan qasa da samun haqqoqin xan qasa daga gwamnati. Don haka ne ba a xauki wannan ilimi sana'a ba ne, amma hujja ce babba ta qarin daraja da matsayi a cikin al'umma.

Irin wannan hali na tauye ilimi da qin faxaxa *shi*, ne ya hana 'ya'yan talakawa da yawa zuwa makarantar Firamare. Ina kangado ga shugabannin da suke son su ga Arewa a hannun 'Yan Arewa, amma kuma ba sa son su faxaxa ilimi don kowa ya samu? A shekarar 1958, wani mai kishin ilimi mai suna Malam Muhammadu Sani Idrisa ya rubuta wasiqa zuwa ga Editan jaridar Gaskiya ta fi Kwabo daga Bauci inda ya haskaka mana halin da ilimi ke ciki, inda ya ce:

Zuwa ga Editor

Bayan gaisuwa, muna so ka roqar mana En'e ta Bauci ta sa a bincika dalilan da suka sa 'ya'yan talakawa ba su cika samun shiga babbar Firamare daga qananan Firamare ba. Duk talakan da ke nan Bauci yanzu hankalinsa a tashe yake qwarai, domin ganin 'ya'yansu ba su samun shiga babbar Firamare.

An yi 'yan shekaru rabon da a ga haka, kwatsam sai ga shi a yanzu an koma irin da. Da ma can abu da talakawa suka riqa kuka ke nan, har aka dube su, aka riqa share masu hawaye, ana sa 'ya'yansu na zuwa babbar Firamare. Sai ga shi a bana an koma kamar da.

'Ya'yan talakawa da ke makaranta qaramar Firamare ta cikin garin Bauci, su da iyayensu hankalinsu a tashe yake. Dalili kuwa, lokacin da aka yi jarabawar zuwa babbar Firamare a bana, da amsar jarabawar ta dawo, sai aka ga galibi duka 'ya'yan malamai su ne waxanda suka yi nasara, 'ya'yan ainihin talakawa kuwa suka faxi.

Wani babban abin da ke qara vata wa talakawa rai, shi ne ko 'ya'yan nan nasu ba su ci jarabawa ba, ga shi kuwa da sauran quruciyarsu, in sun nemi su ci ga ba da koyo, sai a cewai ba dama, tilas ne su bar makaranta a lokacin. To, yaronka ya shekara kamar huxu a makaranta, sai ran nan ka gan shi an sallamo shi, wai bai ci jarrawabawa ba kuma ba dama yaci gaba da karatu, mai kuwa zai hana hankalin ubansa ya tashi?

Har ila yau, in an yi tunani, sai a ga rashin samun shigar 'ya'yan talakawa babbar Firamare ai wata 'yar suka ce a kaikaice ga makaranta. Domin kuwa sauran talakawa idan suka ankara ba a

barin 'ya'yansu su shiga babbar Firamare, lallai hankalinsu zai tashi qila ma har ta kai su riqa qin ba da ya'yansu ga qaramar Firamare xin sam.

Muna gani kamar in ba akwai murxiyan ba, ba zai yiwu a ce duk 'ya'yan talakawan da ke qaramar Firamare ta cikin garin Bauci ba su da haziqancin da za su ci jarabawa ba. Da mamaki a ce sai 'ya'yan Sarakuna, na malamai da na attajirai kawai su ke cin jarabawa, na talakawa kuwa ba sa ci. Ba shakka wannan abu ya isa hukuma ta bincika, ta san irin shirin da ta yi. In ba haka ba muna tsoron kada 'ya'yan talakawa da su talakawan kansu su rasa amincewa da irin jarabawar da a ke yi.

Bai kamata a riqa nuna banbanci a makaranta ba in har ana nunawa xin, domin wurin da aka fi son mai qoqari ne, ba kawai 'ya'yan Sarakuna, na attajirai da na malamai ba. Idan am bincika waxanda suka ci jarabawa a bana, za a iske duk galibansu 'ya'yan Sarakuna, na malamai da na attajirai ne.[1]

Tun kafin Arewa ta samu Mulkin Kai a shekarar 1959, duk kusan 'yan ma'aikatar Hukumar ilimi 'Yan Arewa ne, amma ba a yalwata ilimi ba. Irin tsarin ba da ilimi da Turawan Mulkin Mallaka wato shirin ba da ilimi da bigiren tsarin Hindu, shi 'Yan Arewa ke bi, tun daga wancan zamani har ya zuwa wannan zamani. Saboda ilimi hujja ne na zama babban ma'aikaci mai riqe da babban muqami. A dalilin haka ne ake cewa, 'Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa, ya bayar da wata babbar dama ga 'Yan tsiraru su danne masu yawa', shirin kuma yaci tura. Saboda ana amfani da nasaba da matsayin iyayen yara ne wajen ba su ilimi amma ba qwazo da basirarsu ba, wani abu da ya daqile ci gaban Arewa, wanda jama'a da yawa ba sa son a faxi wannan matsalar ballanta a yi maganinta. Idan har sai 'ya'yan shugabanni da attajirai da malamai ke samun ilimin boko ta ko qaqa, to ana yin haka ne don wannan shiri da zai ba su dama da izzar jagorancin Arewa, amma ba bisa dacewa ko cancanta ba. Bugu da qari, zan qara nanata cewa, 'Yan kwaleji na fitowa da qiyayyar Sarakuna da kuma qiyayyar faxaxa ilimi, domin ilimi hujja ne, wani hali da ake cunkusa masu a makarantun Midil da Kwaleji, wani hali kuma da ya yi mummunan tasiri akan harkar rayuwar jama'a da ci gaban Arewa. An cewanda ya yi abin da yaso, zai ga abin da yaqi. Ga alama shugabannin Arewa ba su sami amincewar jama'a ba, wajen aiwatar da shirin, Arewa A Hannun 'Yan Arewa, domin jama'a na ganin bambanci wajen xaukar yara makaranta da kuma tura su qetare wajen qaro ilimi.

---

[1] GTK 25 ga Afrilu 1958, shafi na 2

Amma ko ana so ko ba a so, ba da ilimi ya zama tilas, idan ana son shirin da ake kurantawa ya samu nasara. Saboda Arewa qasa ce mai faxin gaske da yawan mutane, don haka ba yadda za a ce 'Yan tsiraru sun cika dukkan guraben ma'aikata. Da aka hango lokacin Mulkin Kai da samun 'Yanci sun gabato, za su kuma zo wa Arewa ba tare da ta yi masu kyakkyawan shiri ba, sai aka yi hovvasa wajen qara samar da ma'aikata. A wannan lokaci, sai aka yi hanzarin da ya haifar da nawa, kamar yadda jinkirta bayar da ilimi na wancan lokaci ya zama tarnaqin hana ci gaban qasa da rayuwar jama'a. Shi ne kuma ya maida 'Yan Arewa 'Yan Abamu! marasa katavus a harkokin rayuwarsu.

Yaqin Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa, ya so ya ruxa tunanin waxansu 'yan Arewa. "Waxannan su ne waxanda iliminsu na zamani, bai fi qarfin a rataya wa qadangare ya ruga da shi ba, sai suka fara fartar qasa, wai a kori duk mutanen Kudu a ba su ayyukansu" inji Gwamna Bryan. Yaci gaba da cewa: "Sai da Sardauna ya yi tsaye, ya ce"zama xan Arewa ba shi ne takardar iya aiki ba. Takardar iya aiki ita ce shaidar ilimi, da shaidar goguwa ga aikin. Makaman Bida kuma ya yi tsaye da cewar kada a kuskura a tauye ilimi wai don ana son 'yan Arewa su ja Arewa. Ta wannan tsayawa, ya murje siyasar 'yan Makaranta. Da ma siyasar xalibai, da farko ita ke wahalar da duk qasar da ta sami Mulkin Kai."[1]

Wannan shi ne ihu bayan hari. A irin yadda aka tafiyar da shirin cikin gaggawa babu yadda za a yi a tsananta wajen neman zuzzurfan ilimi ko goguwar aiki. Shugabannin Arewa sun himmatu wajen ganin shirinsu ya kai ga nasara. Daga 1 ga watan Afrilu na shekarar 1958, sai Alhaji Abubakar Imam ya zama zaunannen xan Hukumar Xaukar Ma'aikatan gwamnatin Jihar Arewa. Ita wannan Ma'aikata ke da alhakkin baiwa 'yan Arewa aikin yi ta kuma yi qoqarin baiwa 'yan Arewa ayyuka daban-daban masu dama.

Alal misali, a cikin shekaru biyu (1955 zuwa 1957) an xauki 'yan Arewa xari biyar da sittin (560) qananan matsayi, an kuma xauki xari xaya da xaya (101) a matsayin Siniya Sabis. Ita wannan Hukuma, ta buga rahotanta na farko a Kaduna. Shi wannan rahoto yana xauke da ayyukanta tun lokacin da aka naxa shugaban Hukumar ran 1 ga Nuwamban shekarar 1954 zuwa 31 ga Disamba 1957.

Nasarar da Hukumar ta ci a shekarun 1955 da 1956 shi ne xaukar ma'aikata xari huxu da ashirin da shida (426) da sauran 'yan Nijeriya da 'yan Afirka ta Yamma xari da uku (203) aka xauka aiki. A shekarar 1957 'yan Arewa xari da talatin da huxu (134) da wasu mutane xari da ashirin (120) aka xauka aiki.

An kuma bayyana rashin yawan 'yan Arewa a shekarar 1957, saboda an fi ba da qarfi wajen koyo. 'Yan Arewa da suke koyo ba a nuna su a cikin rahoto ba, sai

---

[1] Alhaji (Dr) Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 80

bayan an xauke su aiki, misali kusan 'yan Arewa xari huxu (400) ke Makarantu Koyon Aikin Akawu daga cikinsu wasu suka kama aikin gwamnati.[1]

Ayyukan wannan Hukuma ne shugabannin Jamhuriyar Farko ke kambamawa wajen nuna kyaun shirinsu na Arewa a hannun 'yan Arewa. Irin wannan aiki ya dace da wannan zamani da kuma shirin al'ummar da ake son ginawa. A yi komai na Arewa don 'yan Arewa ba tare da tsinkayar gaba ba. Shirin sai ya cunkusawa 'Yan Arewa rashin burin neman ilimi mai zurfi kamar ilimin kimiyya na Injiniya da Likita da na Lauya, waxanda suke xaukar shekaru da dama wajen koyo. Hukumar ma bata cika maganar irin waxannan ma'aikata ba. Wata qila, an sallamawa 'yan Kudu su. Amma ayyukan da suka shafi mulki, a nan 'yan Arewa suka shagala, ko kuma aka shagaltarda su.

Tazarar ilimin da Kudu ta ba Arewa bai haifar mata da illa ba kamar yadda aka baiwa Arewa salon ilimin da aiki irin na ta kawai. Da irin wannan shiri ne 'yan Arewa suka shigo sabuwar Nijeriya inda suka fuskanci matsaloli da qalubale iri-iri, ta ko'ina suka rufar mata. Har yanzu bata taso ba, ko da yake an aiwatar da wannan shiri ne da kyakkyawar niyya, amma ya ci tura.

Wani babban qaimin da ya sanya wa shugabannin Arewa yin abin da suke qi, wato yalwata ilimin boko, shi ne la'akari da suka yi, za a yi baya ba zane. Shirin Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa, yana tafiya kafaxa da kafaxa da shirin Ba 'Yan Nijeriya Jan Ragamar Nijeriya. A wajen aiwatar da waxannan shirye-shirye guda biyu masu muhimmanci ana buqatar masu ilimi da ma'aikata waxanda za su cike gurabe masu yawa. Abin takaici shi ne Arewa ba ta da isassun ma'aikata a gida ballanta na ta aika da su ma'aikatun Tarayya. Idan kuma ba ta cika gurabenta na Tarayya ba, to, 'Yan Kudu ne za su cike su ko kuma wasu baqi daga qetare. A nan ma sai ga Arewa na fuskantar mallakar mutanen Kudu a zahiri.[2]

Wannan shiri yaci tura. Ya kuma haifar Arewa matsalaloli masu yawa, xaya daga cikinsu shi ne ya maida ita jemage. Saboda babu shirin bada ilimi kyauta, ba a kuma son 'yan Kudu su mallake guraben aiki a Arewa. To, tafiyar da waxannan abubuwa guda biyu, kishiyoyin juna kuma a lokaci guda sai ya birkita hankalin 'yan Arewa ya kuma kixima su. Domin idan aka yalwata ilimi zai rusa tsarin Ilimi Hujja to, idan ba ilimi kuma, 'yan Kudu za su mallake Arewa cikin sauqi. A dalilin haka ne sai Arewa ta rikixe ta zama jemage.

---

1 GTK 23 Mayu, 1956, shafi na 7

2 *GTK*. 25 ga Afrilu, 1958

Arewa ta Zama Balbela

Tun fil azal an san mutanen Arewa da qwazo da dauriya da dagewa wajen neman duniya, sun kuma yi suna wajen taimakekeniya ga juna. Mutane ne da ke da nagarta da qomaji wajen share wa kansu hawaye tare da kare mutuncin kansu da kansu. A kusan dukkan harkokin duniya baka ganin wallansu basa kuma bada damar da za a karya masu irlinsu. A sabili da haka ne ma M. Abubakar Tafawa Valewa, Wakilin Lardin Bauci a ranar 20 ga watan Janairun shekarar 1947, a zaman Majalisar Wakilai ta Arewa na farko, ya yi alfahari da faxin cewa, "Za mu fara karatun sabon darasi a cikin tarihin Nijeriya ya ci gaba da cewa:

> *Inda Allah Ya taimake mu, mu mutanen Nijeriya ta Arewa, da ma muna da harsashi wanda za mu iya aza kowane irin gini na mulki a bisansa. Ga mu da dokokinmu, ga mu da irin samfurinmu na mulki, ga mu da dabarunmu na zaman duniya, ga mu da al'adunmu waxanda su ke ababan sha'awa. Abin da kawai su ke buqata, shi ne a dai-daita su da zamani. Ko da shi ke waxansu daga cikin al'adun wajibi ne mu buxa qofofin mu, domin sabbin dabarun zaman duniya su sami shiga. Gurina shi ne Arewa ta canza, ta zama sabuwar Arewa ta zamanin yanzu. Ba abin da raina ke xar-xar a gare shi, sai kada a yi kuskure, a gina wata irin Arewa mara asali, wadda za ta zama jemage, ita ba tsuntsu ba, ita ba dabba ba![1]*

A Arewa an xauka ilimin boko ilimi ne na samun mulki da muqami ba ilimi ne na sana'a ba. Irin wannan ilimi wato *Colonial Education* shi ne ya rikirkita harkar Arewa ya birkita lamurranta sashe-sashe masu gaba da juna ya kuma maida mai iliminta Musulmi mai halin Hindu saboda tsarin Jajmananci da Arewa ke bi sau da qafa. Saboda haka ne bayan kusan shekaru xari da wannan ilimi sai Arewa ta yi birgimar hankaka ta zama balbela wadda bata iya sarrafa komai da kanta sai da taimakon wata dabba.

Nijeriya ta Arewa ta samu so da qauna da kishi tare da kulawa da shugabannin siyasar farko. Waxannan shugabanni sun yi duk abin da za su iya yi don ganin an gina sabuwar Arewa mai karsashi wajen ayyukan ci gaban qasa da nuna qwazo wajen aiki, da gaskiya, da riqon amana wajen shugabanci. Sun guji yin kuskure wajen gina wata irin Arewa wadda M. Abubakar Tafawa Valewa ya misalta da

[1] Abubakar Imam, Auren Zobe, shafi na 42.

"Jemage." Amma abin da ake gudu shi ya auku. Arewa ta zama balbela. Wadda ta fi jemage lalacewa.

A wajen gina sabuwar Arewa sai aiwatar da shirin, "Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa, ya zama kuskure da ya taimaka wajen maida Arewa balbela saboda rashin qulla fus don lalaci da son taimako. Sir Bryan ya yi nuni da cewa yin haka a rashin kangado ne, abubuwan da suka biyo bayan baiwa 'Yan Arewa jagorancin Arewa, sun gaskata wannan imanin nasa.[1] Domin a xan qurarran lokaci ake so Arewa ta samu isassun ma'aikata a cikin shekara goma kacal. Amma kuma ba a son faxaxa ilimi da sauqaqa samunsa ga kowa. Wannan hali sai ya haifar da tufka da warwara.

Sir Ahmadu Bello wanda ya jagoranci wannan shiri, ya yi shi ne da kyakkyawar niyya da manufa, yana da imanin 'yan Arewa za su kai Arewa inda yake nufi, ko yana raye ko kuma bayan ransa. Yana da imanin cewa 'yan Arewa ne suka fi cancantar mulkin Arewa. Firimiya bai tava mafarkin wasu 'yan Arewa za su maida Arewa saniyar tatsarsu ba. Haka kuma bai tava mafarkin wasu 'yan Arewa za su sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Kudu ba. A duk ayyukan da ya yi wa Arewa, wannan shiri kamar shirin Aiki da Ibada ba su tasiri ba. Sardauna da 'yan Majalisarsa sun yi imani da cewa kamar yadda suka sadaukar da kansu wajen gina sabuwar Arewa, haka waxanda za su ba jagorancin Arewa za su yi. Wannan kuskure ne saboda ba su da tabbacin masu gadon su, za su taka rawa irin tasu. Domin idan aka baiwa waxanda ake ganin amintattu ne ragamar jagorancin Arewa, wato giyar mulki ka iya sa su ci amanar Arewa.

Saboda haka a irin wannan hali, abin da ya kamata a yi shi ne a bar Arewa ta qwaci 'yancinta da kanta daga 'Yan Kudu. Idan shugabanni suka shiga yarjejeniya da shugabannin Kudu suka kuma sami goyon bayan qasar Ingila, sai su duqufa wajen sauqaqa ilimi da faxaxa shi domin samun isassun ma'aikata da masu ilimi cikin shekaru ashirin. Da ilimi da sana'a ake qwatar 'yanci babu yadda za a iya danne al'ummar da ta ginu akan su. Kamar yadda Sir Bryan ya ce sun yi imani a rayukansu cewa tatsar da mutanen Kudu su ke yi wa Arewa ya isa haka nan. Domin haka sai su ka shiga wannan yaqin baki buxe, ido rufe, kunne rufe, wurin baiwa 'yan Arewa jagorancin Arewa. Amma sai ga shi shirin ya birkice ya maida Arewa jemage! Yan Arewa sun yi birgimar hankaka sun zamasu ba 'yan Kudu ba ba kuma 'yan Arewa ba!

Da aka samu Arewa a hannun 'Yan Arewa ana iya cewa tatsar da 'yan Kudu kewa Arewa ya ragu kaxan, amma kuma tatsar da 'Yan Arewa ke yi wa Arewa ya qaru ya kuma yi tsanani sosai. Harila yau ana iya cewa abin da wannan shiri ya haifar shi ne danniya da 'yan Arewa ke yi wa 'yan Arewa, wanda ya fi danniyar 'Yan Kudu muni da illa. Domin gwagwarmayar gudu daga mallakar 'yan Kudu ta

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 42

jefa Arewa cikin wani kurkukun Mulkin Mallakan 'yan Arewa. Ba da mulki ya haifar da rashin kishi tare da qyamar dacewa da cancanta wasu halaye da ke kawo ci gaba ga al'umma. Haka kuma mulkin jama'a ba tare da kishinsu ba shi ya taimaka wajen maida Arewa jemage, ita ba tsuntsu ba, ita ba dabba ba. A dalilin haka ne ma wasu ke cewa Arewa ta mutu. Sai ta zama balbela wadda ba ta iya neman abinci da kanta sai da taimakon wata dabba. Ita wannan dabbar ce za ta riqa agaza mata da fari ko qwari ita kuma tana bi tana kamawa sannu a hankali. Amma idan ta fit aneman abinci ba ta sami taimakon wata dabba ba sai ta kwana da yunwa. Don kuwa tana ji tana gani fari na fareti a gabanta ba ta iya yin komai sai kallo saboda lalaci.

Mulki da adalci abu ne mai muhimmanci da kuma tasiri ga ci gaban al'umma. Saboda ba a ba da shi ga wanda yake da zalamar bixarsa sai dai a same shi bisa qwazo da dacewa da kuma cancanta. Idan aka cire dacewa da cancanta aka ba da mulki ga waxanda ba su dace ba, to, babu shakka shirin ba zai haifar da xa mai ido ba. 'Yan Arewa sun san haka amma "duk da kangadonsu, suka qi Kangado", in ji Sir Bryan.[1] Wannan harsashe nada alamar gaskiya domin yanzu 'yan Arewa da neman taimako suke rayuwa ba da ci da guminsu ba, ba kuma da dogaro da kansu ba. Sun kuma shagala wajen dogaro da maqwabtansu a fagauniyarsu ta hannu da miya shi ake bi da lasa!

A cikin wannan mulki ne "naka na jikinka ne tarnaqin hana ke ci gaba"! Kafin Arewa ta kai ga wannan mummunan hali kuwa an xauka "naka-sai-naka." Amma a yanzu an samu juyawar al'amari da zamani ya kawo. Saboda haka tilas jama'a su lura da cewar "naka-naka ne" in ya nuna ta hali da aiki" naka ne." In kuwa ba haka ba, to, ka saurara "naka ba-naka ba ne." Saboda zamani ya birkita qwaqwalwar xan Arewa, ya yi watsi da xabi'u da al'adunsa masu kyau ya rungumi na 'yan Kudu. Abin takaici sai ya kasa zama xan Kudu amma kuma shi ba xan Arewa ba ne na asali, domin ya zama jemage. Ya yi vatan-vakatanta!

Su kuma 'yan Kudu a fagauniyar neman zama Turawa sun yi watsi da xabi'u da al'adunsu sun kuma rungumi addinin Turawa amma sun kasa zama Turawa. Saboda haka su ma sai suka yi vatan vakatantan. Abin takaici kuma sai Turawa suka xana masu karen-tsana suka kuma aibantasu suka kira su Fitsararrun Qabilun Bakin Teku. Wato Arewa ta zama jemage Kudu kuma ta zama fitsararriya! Arewa kuma ta zama jemage. Saboda haka sai Nijeriya ta ruguntsume.

Wannan shiri shi ya kawo salon mulkin jama'a ta kan waxanda ba su dace ba. Tun da ana bada shi ga masu zalamar bixarsa, har ya kai a yanzu qwatar mulki ake yi ta kowane hali. Wannan hali kuma ya kawo wani sabon salon shugabancin jama'a amma ba tare da kishinsu ba. Ya kuma cire himma da qwazo wajen neman mulki na nuna kyaun hali, adalci da karimcisaboda ba da shi ake yi kawai ga

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 71

waxanda ake so ba waxanda suka dace ko suka cancanta ba. Bugu da qari wani babbar illa da ya haifar ita ce ta rashin qulla fus ga akasarin 'yan Arewa Musulmi waxanda suka zama "Yan A bamu"! A bamu kwangila, a bamu aiki, a bamu mulki! Irin wannan hali ya kashe sana'a ya kuma haifar da lalaci da tumasanci saboda mutuwar zuci da kuma dogaro da gwamnati, wadda ita ce da alhakkin baiwa jama'arta abubuwan more rayuwa da duk al'amuran da suka shafi ayyuka da kasuwanci da harkokin mulki. Waxannan illoli sai suka fara hudo kai a zamanin Firimiya. Hali irin na balbela ya qasqantar da 'yan Arewa a idanun 'yan Kudu waxanda suke tuqahon cewa in ba su 'yan Arewa za su halaka. Domin su 'yan a bamu ne masu hannu a qasa.

Kafa Hukumar Xaukar Ma'aikata a cikin wannan shiri na 'Ba 'Yan Jagorancin Arewa', ke da wuya sai Sir Ahmadu Bello ya fara ganin irin abin da shirin zai haifar. Zai maida 'yan Arewa balbela. Saboda ana ba da sanarwar kafa wannan hukuma, sai ta jawo samun takardun neman aiki dubbai, amma ba neman qaro ilimi ko sana'a ba. Saboda haka, 'yan Abamu sai suka yi wa wannan ma'aikata xango. Ita wannan ma'aikata sai ta kawo rububi daga jama'a waxanda suke son a basu aiki. A dalilin haka ne sai Sardauna, ya yi bayani a kan hudowar wannan sabon lamari. Ga abin da ya ce a Majalisa:

"…ina son in gargaxi 'Yan Majalisa, su san cewa zama xan Arewa kurum ba tare da isasshen ilimin da ake buqata ba, ba zai sa a xauki mutum aiki ba. Waxansu mutane sun xauka a rayukansu cewa tun da yake su mutanen Arewa ne, ai babu dalilin da zai hana a ba su aiki. Su kan ce ai sai a ba mu don mu 'Yan Arewa ne: Idan mutum shi xan Arewa ne na asali, to, ya tabbatar wa duniya. Haka nan mana, cewa shi irin mutanen nan ne da suka yiwo kan gaba don taimakon jama'a, ba don taimakon kansa ba. Ina so in tabbatar wa 'yan wannan Majalisa cewa gwamnati ta niyyar ta hanzarta danqa wa 'Yan Arewa jagorancin Arewa cikin gaggawa. Don haka ne mu ke ta qara taimakon dukkan xaliban da suka nuna suna so su je qasashen qetare don qaro, kuma dalilin haka ne ya sa muka dage, kai da qafa, muka ce sai a kafa mana Hukumar Xaukar Ma'aikata tamu ta kammu a wannan Jiha, don mu sami tsare Arewa ta zama ta 'Yan Arewa."[1]

Sardauna ya fahimci tun a farkon wannan shiri cewa ba zai cimma muradinsa ba saboda ganin yadda 'yan Abamu suka yi wa Ma'aikatar Xaukar Ma'aikata xango. Ya kuma lura irin waxanda suke hanqoron a basu ba safai suke da halin 'Yan Arewa na asali ba, don haka ne ya qalubalance su da cewa, "Idan mutum shi xan Arewa ne na asali, to, ya tabbatar wa duniya haka nan mana, cewa shi irin

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 184

mutanen nan ne da suka yiwo kan gaba don taimakon jama'a, ba don taimakon kansu ba." Samun irin waxannan 'Yan Arewa na asali, sai ya zama nadiri. Saboda haka hanzarta danqa wa 'Yan Arewa jagorancin Arewa cikin gaggawa, sai ya zama an yi gudun gara ne aka faxa zago. Shi ne ya maida 'yan Arewa masu dogara ga gwamnati ba ga kansu ba. Ya kuma maida su balbelu wajen rashin dogaro da kai saboda lalaci da rashin karsashi. Don haka ne ake wa balbela kirarin, "Mai kyaun banza".

Gwamnati ta taimaka wa xaruruwan 'Yan Arewa zuwa qetare wajen qaro ilimi, a wani hovvasa da ta yi wajen horar da ma'aikata amma saboda rashin samun tantance xalibai domin tura waxanda suka dace ya sa wannan shiri bai xore ba. Ana ba da guraben qaro ilimi ne ga akasarin xaliban don suna 'Yan Arewa, abin da Sardauna ya yi gudun ganin ya auku. Firimiya ya tsare Arewa don ta zama ta 'Yan Arewa, su kuma su tsare ta don ta zama ta 'ya'yansu. Saboda kaxan ne suka fito suka tabbatar wa duniya cewa su 'yan Arewa ne na asali, waxanda suka yiwo kan gaba wajen taimakon jama'a ba wajen taimakon kan su ba. Haka kuma ba za a manta da wasu 'yan Arewa da suka sayar da qasarsu ta gado ga 'yan Kudu ba. Saboda zakwaxin son mulki da dattin duniya! A wannan al'amari "naka-naka-ne" in ya nuna "naka-ne" ta hali da aiki.

Idan da an himmatu ne wajen gina jama'a kamar yadda aka yi da farkon farawa da 'yan Arewa sun qwaci 'yancinsu daga mallaka da tatsar 'yan Kudu. Duk da kururuwar Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa da aka daxe ana yi bai hana 'Yan Kudu ci gaba da tatsar Arewa ba, sai ma suka maida ita wata kasuwa a ciki a watse. Kusan ace a yanzu kowane xan Arewa yana da xan Kudu da ke tatsar sa. Don haka ma sai suka kwararo cikinta suka riqe sufuri, da kasuwanci da makarantu da harkokin ilimi a wannan zamani. Sir Abubakar Tafawa Valewa, Firayim Ministan Nijeriya ne ya tava yin qorafi da yadda 'yan Kudu ke kwararowa zuwa Arewa a Majalisa.[1] Wato waxannan shugabanni sun hangi abin da suke gudu shi zai auku. Abin takaici kuma shi ne ba mallakar Arewa 'yan Kudu suka yi ba kurum, 'yan Arewa sun dogara ne kacokan ga 'yan Kudu don su ne Masu Tsaronsu, Likitocinsu kuma Malaman 'ya'yansu a makarantunsu.

Har ila yau a wannan zamani Arewa sai ta yi birgimar hankaka ta zama balbela wadda saboda tsananin lalaci da son jiki bata iya neman abinci sai idan da dabba wadda za ta bi tana tayar mata da qwari, ita kuma tana bi tana kamawa. Idan ta fito kiwo bata samu dabba ba sai ta koma gida da yunwa, ba don rashin qwari ba amma don rashin dabbar da zata taimaketa kamawa. Abin takaici shi ne 'yan Arewa ba su da sana'a tasu ta kansu, sun dogara ne kacokan ga 'yan Jihar Gabas da 'yan Jihar Yamma wajen rayuwa kamar yadda balbelu suka dogara ga dabbobi wajen kiwo. Kamar yadda dabbobi suke ga Balbelu, haka 'yan Kudu suke

[1] *The Makers of Northern Nigeria*, shafi na 32

ga 'yan Arewa! A lokacin ake fafitikar tsare Arewa ga 'yan Arewa, sai ga qurar ba 'yan Nijeriya jagorancin Arewa ta taso ta turniqe

Ba 'Yan Nijeriya Jan Ragamar Nijeriya

An ce idan duka ya yi yawa na ka akan kare. Saboda rashin isassun ma'aikata, sai aka baiwa shirin Ba 'Yan Arewa Jagorancin Arewa fifiko wajen aiwatarwa da gaggawa. Wannan ya sa sai 'Yan Arewa kaxan ke aikin gwamnatin Tarayya. A dalilin haka ne aka sami kashi xaya cikin xari na 'Yan Arewa ke aikin gwamnatin Tarayya ta Nijeriya. Wannan matsala an yi magana kanta cikin rahoton farko da mai kula da sha'anin Ba 'Yan Nijeriya Jan Ragamar Nijeriya ya bayar a Ikko a shekarar 1958. Rahoton ya ce ana iya qiyasta girman wannan sha'anin idan aka duba cewa yawan 'yan Arewa ya kai kashi hamsin da biyar (55%) cikin xari na mutanen Nijeriya duka. Amma kuma kashi xaya cikin xari (1%) na 'yan Arewa ke aiki a federa.

Daga nan rahoton ya jera wahalhalu guda bakwai da a ke sha wajen samun 'Yan Arewa su shiga aikin gwamnatin Tarayya. Na farko, yawan masu fita makarantun Sakandare a Jihar Arewa kaxan ne. Na biyu, waxannan 'yan Sakandare da za a iya samu, gwamnati, ko En'e-En'e su kan xauke su duka cikin ayyukansu, ko kuma a kan ba su sikolashif don qaro ilimi. Na uku, an fi xaukar mutane masu qarancin ilimi aikin gwamnatin Jihar Arewa fiye da matsayi irin waxannan a gwamnatin Tarayya ta Nijeriya. Wato Arewa ba ta da masu ilimi da za su riqe muqamai masu daraja a federal. Na huxu, sikolashif na Jihar Arewa don qaro ilimi qasashen qetare sun fi sikolashif na gwamnatin Tarayya, don kuwa ta waxansu lokuta su kan baiwa wa mace tallafi don ta tarar da mijinta kirki da ke can qetare, a sa'an nan kuma su xaliban su kan zo Nijeriya lifi idan Kwas xin nasu mai tsawo ne. Irin wannan garavasar da su ke samu, ya sanya aka yi watsi da sikolashif na *Federal*, aka kuma daxe 'yan Arewa ba sa amfana da wannan tallafi na gwamnatin Tarayya.

Dalili na biyar, shi ne akwai damar samun ci gaba a aikin gwamnatin Jihar Arewa fiye da na gwamnatin Tarayya. Na shida, mutumin da zai kama aikin gwamnatin Jihar Arewa da qaramin ilimi ba zai zama xaya da aikin gwamnatin Tarayya ba inda zai shiga gasan samun ci gaba tare da waxanda su ke da ilimi sosai. Na qarshe, shi ne an ga dai 'yan Arewa sun fi so su yi aiki a Jihar Arewa da su ce za su yi a Ikko ko wani wuri daban.[1]

A tashin farko wajen kafa sabuwar Nijeriya 'yan Arewa ba su tavuka wani abin a zo a gani ba, a duk lokacin da suka sami wani qalubale sai su noqe masa, su nemi wata hanya mai sauqi da za su bi domin gudun wahala. Amma gudun wahala ba shi maganinta ba, fuskantarta shi ne magani. A tarihin Arewa ba inda

[1] GTK Ta 851, 30/5/1958

'yan Arewa suka zama ragwaye kamar wannan zamani mai haxari da qalubale iri-iri.

A wancan zamani duk da garavasar da ke akwai a aikin *federal* sai suka yi biris da shi, don yana buqatar ilimi mai zurfi tare da gasa da nuna qwarewa. Bugu da qari kuma, sai zuwa Ikko ko wani gari a Kudu ya zama wani jihadi babba sai qalilan su ke yi. Amma 'yan Kudu da suka fahimci Arewa na da abubuwa masu yawa da 'Yan Arewa ba su iya yi, sai suka riqa kwararowa suna mamaye harkokin kasuwanci da sana'oi iri-iri. Wato sai suka rusa bangon da ya Tsare Arewa Don 'yan Arewa. A wannan lokaci kuwa 'Yan Arewa kifayen rijiya ne, sai dai a nemo abinci, a ba su don ba su zuwa ko'ina. In sun bar gida kuma sun zama nama ke nan. Amma kuma wannan ba shi ne halin 'yan Arewa na asali ba. Don sun yi suna wajen sufuri da kasuwanci a qasashen duniya kafin zuwan Turawa.

Rahoton da ya yi kyakkyawan bayani akan rashin samun 'Yan Arewa a aikin gwamnatin Tarayya, ya qara da cewa am ba da shawarwari guda shida ta yadda za a xauki 'yan Arewa aikin gwamnatin Tarayya. Game da muqaman Siniya Sabis, dole ne a faxi gaskiya cewa kusan dukkan guraben da ake da su an cika su. Ko da ba a cika su ba, 'Yan Arewa sun fi son zama a Arewa, don a nan ne ake masu fadanci, suke kuma raya tumasanci, duk da gwagwarmayar da aka xauka ta cunkusawa 'Yan Arewa aqidar Aiki da Ibada wanda bai yi tasiri ba. Saboda shirin Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, ya cunkusa masu ra'ayin xan Arewa ba shi a ke yi, ba nema wa kansa yake yi aiki ba. Waxannan shiri guda biyu sai suka riqa tufka da warwara. Da wannan ra'ayi na abamu don muna 'yan Arewa, babu wanda zai kula su a wajen aikin gwamnatin Tarayya inda ake karo da karon ma'aikata qabilu iri-iri da gasa wajen nuna ilimi da qwarewan aiki.

A lokacin da ake fafitikar aiwatar da wannan shiri, babu wanda ya hango yin haka zai kashewa 'yan Arewa kuzari da nagarta wajen neman abu da kansu ba tare da nuna lalaci ba. Sai ace komai kyawon niko bai kai nunan sama ba! Da yake ana aiwatar da wannan shiri ido rufe kuma kunne rufe ne, da kuma niyyar ba da ragamar jagorancin Arewa ga waxanda ake zaton za su gina ta, sai aka shiga kuranta wannan shiri ana kuma kambama shi don ya sa mu karvuwa. Amma duk inda aka dosa sai a cimma matsaloli, sai kuma ayi biris da su.

Manufan nan ta gwamnati ta mai da dukkan ayyuka hannun 'Yan Arewa sai aka yi masa qaimi, aka ci gaba da shi, da duk iyakar qarfin gwamnatin Jiha. Aka kuma gaggauta qoqarin naxa 'Yan Arewa aikin Di'o-Di'o da sauran muqamai. An yi qoqari na musamman wajen zavo 'Yan Arewa da aka naxa su muqamin Di'o-Di'o. Aka kuma aika da su larduna. Sardauna wanda yake shi ne limamin wannan shiri ya ce:

"Har ila yau kuma, na amince Majalisan nan za ta yi farin ciki da sanin cewa lauyoyin farko 'yan Arewa guda biyu da aka aika da su qaro ilimi Ingila, bisa

shirin qaro ilimi na gwamnatin Nijeriya, sun ciwo nasara sun komo Arewa kwanan nan. Ba ma sai am faxa ba, cewa an xauke su a cikin aikin gwamnatin Jihar nan.[1]

A lokacin gina sabuwar Arewa ba a maganar dacewa da cancanta sai nadiri, abin da aka fi raja'a akai shi ne naxa wa da badawa a kusan duk harkokin da su ke neman dacewa da cacanta. Don haka sai wannan hali ya zama jiki, ya kuma cire wa 'Yan Arewa qwazo da nuna nagarta wajen neman muqami. Don waxannan halaye ba su da tasiri sai an haxa da tumasanci da fadanci kafin likkafar ma'aikaci ko xalibi ta yi gaba. A nan sai ace gaggawa wajen ba da duk ayyukan jihan Arewa ga 'yan Arewa ya haifar da nawa tare da nadama. Bugu da qari wajen ilimi, ba a maganar xalibai masu yawa, sai 'yan qalilan. To me lauyoyi biyu kacal za su yi wajen gina Arewa ko Nijeriya? Don a yanzu 'yan Arewa ba su da wata izza da nuna gwaninta a fannin ilimi ko sana'a a Nijeriya. An duqufa wajen horar da Akawuna, da bayar da ilimi don ci gaba, da habaqa yaqi da jahilci, da kyautata hanyar noma da inganta zaman jama'a.[2] Amma saboda nuna son rai, da xaukaka nasaba sun kawo tarnaqi babba wajen ciyar da Jihar gaba. Bugu da qari yawan waxanda Arewa ke fitarwa basu isa su cike guraben da ake so ma'aikata su cike ba. Ana cike wasu ana kuma barin 'Yan Kudu ko kuma baqin qetare su cike su. To, sai aka wayi gari rashin ilimi da masu ilimi wadatacce ya wofintar da shirin Tsare Arewa Don Yan Arewa. Ko kaxan wannan bai nuna shirin ba shi da fa'idaba. Shiri ne da ya baiwa Arewa kyakkyawan harsashi saboda yana kyakkyawar manufa.

Kyakkyawar Manufa

Game da qananan ma'aikata, waxanda ake buqata da gaggawa sai aka kafa Makarantun Koyon Aikin Akawu guda huxu a shekarar 1956, waxanda aka shirya don su qara yawan ma'aikatan akawu-akawu 'yan Arewa ainun, waxanda Jihar nan take talaucinsu. Sai aka ga kuma ya zama a fuskanci gaskiyar cewa, duk da qoqarin yawon neman ma'aikata ko'ina a Jihar nan da wani goggagen ma'aikaci xan Arewa, ya yi a shekarar 1955, 'yan Arewan da aka samu masu ilimin da ya cancanci su iya shiga aikin gwamnati, 'yan qalilan ne. A saboda haka ne Sardauna, ya ce: "Cikin jawabina na bara, na yi maganar matsanantan wahalhalummu na game da samun ma'aikata daga qetare. To, cikin 'Yan watannin nan na baya, ina tsammani musamman saboda Jihar nan, da halayen kwaxaitarwata, an tallata su sosai a qasashen waje, halin nan ya canja ainun.

---

1 GTK Ta 851, 30/5/1958

2 *Ibid*. 6 Maris, 1956.shafi na 2

Hasali ma dai yanzu ginin gidajen ma'aikata shi ne babban aikin da aka fi gabatarwa wajen gine-gine a Jihar nan."[1]

A cikin irin wannan gudu da gaggawa ne ake xaukar tumun-dare idan an tafi wajen neman ma'aikata. A wani lokaci sai aga ashe duhu ne ke dukan duhu. Saboda ma'aikacin bai fi waxanda yake wa aiki da komai ba. An xauki tatsar da 'yan Kudu ke wa 'yan Arewa da tsanani don haka sai aka tafi a guje aka xauka wannan gwagwarmayar ce mafita.

Shirin Ba 'Yan Arewa jagorancin Arewa, ya jefa wannan jiha ga dogaro da baqin ma'aikata daga qetare musamman Turawa daga Ingila. A dalilin haka ne sai wannan jiha ta xanxana kuxarta, a lokacin yaqin duniya na Biyu. Saboda a wannan lokaci ne xaruruwan ma'aikata Turawa da suke aiki a Arewa, suka ajiye ayyukansu suka amsa kiran qasarsu, suka shiga aikin soja don su yaqi Hitler. Nijeriya ta Arewa ta sha wuya ainun a lokacin wannan yaqi a shekarar (1939 – 1945).

A wannan lokaci Malam Shehu Shagari yana xalibi a kwalejin Kaduna ya ce, ba zai tava mantawa ba da yadda yaqin duniya na biyu, yaqin (Hitler) ya haifar da matsaloli da suka shafi xalibai a makarantu ba. Ya ce sun fuskanci karancin malamai, babu kamar malamansu Turawa waxanda guguwar masifar yaqin ta sa aka janye su daga xakunan karatun xalibai domin shiga ayyukan soja. A wannan lokaci ne aka fara turo waxansu 'yan asalin Jihar Kudu masu ilimin boko domin su maye makwafin Turawa a makarantun Jihar Arewa.[2]

A dalilin haka ne sai aka samu givi babba na rashin ma'aikata a ofisoshin gwamnati, da makarantu, da asibitoci da sauransu. To, an ce idan ruwa ya ci mutum ko takobi ka bashi sai ya riqe! A cikin wannan mawuyacin hali da Arewa ta shiga, tana ji tana gani shirinta na Tsare Arewa don 'Yan Arewa ya shiga rushewa a hankali kamar runfar kara! A wannan lokaci ne 'yan Kudu suka riqa kwararowa zuwa Arewa suna riqe muqamai masu muhimmancin gaske. Wannan hali ne ya baiwa 'yan Kudu damar mallake Arewa muxlaqan! Da an bar 'yan Arewa a hannun 'yan Kudu, tun farko, ai shekara dubu na raba bawa da bauta. Don kuwa komai tsanani 'yan Arewa za su iya zuwa makarantu a Kudu su ko yi sana'o'i na zamani su kuma sami horon ayyuka iri-iri musamman na akawuna da kiwon lafiya da makamantansu. Idan aka sami shekara goma, 'yan Arewa za su iya samun qarfin gwagwarmayar qwatar 'yanci daga 'Mulkin Mallakar mutanen Kudu. Hasali ma dai, wannan gwagwarmayar za ta qara wa, 'yan Arewa kishi, da qwazo da himmatuwa wajen dogara da kansu, kamar 'yan Kudu, ba dogaro da

---

[1] GTK 6 Maris, 1956.shafi na 2

[2] Sagir Muhammad da Aliyu Isma'ila, *Tarihin Shehu Shagari*, M&I Essence Publishers, Kaduna, (2003) , shafi na . 25

gwamnati ba. An kashe maqudan quxi wajen tura 'yan Arewa qalilan zuwa qetare wajen qaro ilimi, bayan ana iya ba su horo iri-iri a kudancin wannan qasa ko kuma a qasashe a Afirka kamar qasar Ghana, da Sudan da Masar.

Amma duk inda aka bi wajen samun nasarar wannan yaqi, sai a tarar da tilas a yi da 'yan Kudu ko ana so, ko ba a so saboda zamantakewar Haxaxxiyar qasar Nijeriya. 'Yan Kudu kuma sun xauki Arewa akushin tuwon su ne. Don haka nuni ga 'yan Kudu ne maqiyan 'yan Arewa da kuma cunkusa wa 'yan Arewa, cewa za su sami sauqin al'amuran rayuwa idan suna qarqashin mulkin 'yan Arewa bai haifar da xa mai ido ba. Domin kuwa samun mulkin Arewa a hannun 'yan Arewa, sai ci gaban Arewa ya tavarvare bayan mutuwar Sardauna da rundunansa na 'yan siyasa tingantacciya. A yanzu da 'yan Arewa sun zama 'yan Abamu don muna 'yan Arewa, bara da tumasanci sun yi masu katutu Arewa, kuma ta zama kidahuma. Saboda haka take dogara kacokan ga 'yan Kudu.

Ko da yake gwagwarmayar Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, yana da kyawawan manufofi don ya qarfafa abubuwa masu yawa, amma saboda ya cire wa 'yan Arewa qwazo da kishi, sun rushe bayan su Sardauna sun yi shahada. Alal misali, Ma'aikatar Yaqi da Jahilci, wadda tare da Ma'aikatar Talifi wato NORLA da Ma'aikatar Sha'anin Mulki, duk sun nuna gwajin ayyukansu, mai bam mamaki a hovvasan farko wajen ciyar da Arewa gaba, amma yanzu sun dushe muguwar dushewa, kamar sauran ma'aikatu da masaqu domin rashin kishi tare da sakacin waxanda shirin ya baiwa ragamar jan su.

Bugu da qari sashin Kula da Lafiya ma, an yi qoqarin kafa harsashi mai qarfi, amma a nan ma an sami cikas saboda rashin samar da horarrun qananan ma'aikata ya tauye ci gaba. Duk da haka a xiba na biyu na mataimakan likitoci da ake horo, sun fara koyon aikinsu a Makarantar Midil ta Kano, a shekarar 1956. A wannan lokaci ne kuma gwamnatin jiha, ta duqufa wajen gina makarantun Horon farko na masu Aikin Jiyya a Makurxi da Kaduna, da kuma Makarantar Horon Mataimakan Aikin Asibiti a nan Kaduna. Ita wannan makaranta ta Mataimakan Aikin Asibiti, an shirya ta ne, don kyautata horon ma'aikatan En'e da na gwamnati na Asibiti, da Aikin Lafiya na qauyuka, domin ana son a qara shigar da Ayyukan Lafiya da ilimin kiwon lafiya a qauyukan Jihar nan. Duk waxannan kyawawan manufofi ne.

Gwamnatin su Sardauna ta yi qoqarin ganin 'yan Arewa sun tsaya da qafafun su dimir dimir, don harsashin da gwamnati ta shimfixa, zai sanya Arewa ta dogara da kanta. Amma saboda kitso da qwarqwatar da aka yi da shi, ya wargaza wannan tsari. A halin yanzu, 'yan Arewa taron tsintsiya ne shirim, ba shara! Saboda 'yan Arewa na dogaro ne ga 'yan Kudu, a kusan duk harkokin rayuwa, abin da Sardauna ya yi gudun sa kamar mutuwa. Amma saboda an ci amanarsa, sai 'yan Arewa da aka baiwa jagorancin Arewa suka maida ita saniyar tatsa, suka kuma haxa kai da 'yan Kudu wajen tatsarta.

A harkar mulki ma gwamnatin Sardauna ta kafa kyakkyawan harsashin fitadda Akawu-Akawu gwanayen mulki waxanda ka iya aiki a ma'aikatu da ofisoshin gwamnati ba a Arewa ba har ma a sauran jihohin qasar nan baki xaya, kamar yadda 'yan Kudu ke turo ma'aikata masana ilimin kimiyya don su yi aiki a Arewa. Ita ma Arewa za ta iya aikawa da masana mulki a waxannan jihohin. Amma sai sha'anin mulki inda 'yan Arewa suke nuna gogewa da nuna adalci, ya tavarvArewa da hanzari bayan rasuwar Sardauna. A nan ma sai albasa ba tayi halin ruwa ba saboda sai aka wayi gari 'yan Arewa sun yi qaurin suna wajen tafka ta'asa a harkar mulki.

Aikin gona shi ne babban sana'ar Arewa. Sardauna ya nuna kyakkyawar manufa don haka ne, ya samar da ingantattun hanyoyin noma, da ingantaccen iri, da ingantattun hanyoyin hana qwari da hana cuce-cuce, waxanda wajibi ne ga sana'an nan. Don haka ne manoma suka sami kyakkyawan harsashi a cikin wannan shiri da shugabannin Arewa suka baiwa muhimmanci. Saboda wannan dalili, sai a cikin shekarar 1957, aka qara maida hankali ga binciken da yake wajibi, na kayan gonar fitarwa zuwa wata qasa da na abinci, da kuma makiyaya mai kyau.

Sha'anin kyautata abinci shi ma ba a qyale shi ba, don muhimmi ne ainun a Jihar Arewa, inda halayen yanayin qasa ba su da tabbas. A nan ma an nuna kyakkyawar manufa don aji da matsalolin nan musamman na Qasashen Bakin Koguna, sai aka kafa Makarantar Gona a can Alal misali, Makarantar Aikin Gona ta Samaru, na da Malaman Gona talatin da bakwai da Mataimakan Turawan Gona goma sha-huxu da Malaman Gona En'e goma sha-tara, a shekarar 1959. Haka kuma matakin hana cuce-cuce shi ne muhimmin abin da Ma'aikatar Dabbobi za su ci gaba da himmatuwa da shi. Misali, yawan dabbobin da aka yiwa maganin ciwon barci a shekarar 1956 sun kai yawan dubu tamanin (80,000).

Sun kuma wuce sulusin miliyan guda a qarshen wannan shekara. A wajen aikin daji kuma, nufin gwamnatin Sardauna ta qara yawan dazuzzukan jihan. A shekarar 1957 – 58 akwai Dawan Gwamna mai faxin murabba'in mil dubu ashirin da shida da xari shida da tamanin da biyar (26,685) da kevavven wurin gwamnati mai faxin murabba'in mil xari takwas da sittin da uku (863).[1]

A gawurtaccen shirin wannan gwamnati, Arewa ake nufin ta ciyar da qasa baki xaya da kayayyakin gona, iri-iri da kiwon shanu da dabbobi da kaji. Don kuwa Arewa ce 'Nagge daxi goma'. Saboda haka sai a yaba wa wannan gwamnati wajen nuna misali da kyakkyawar manufa.

A fuskar raya zaman jama'a, kuwa gwamnatin Jiha ta matsu ainun da son ta ga ta xaga matsayin zaman jama'a, musamman a alqaryu inda jama'a su ke yin cikowa a wancan zamani. Saboda samun wannan, za a kafa aikin ginin gidaje,

[1] *Kai Da Yanzin Nijeriya*, shafi na 18

bisa babbar harkar jagora a nan Kaduna, tare da haxa kai da waxansu masu harkar kansu. Irin wannan kishi da son jin daxi da rayuwar jama'a da Sardauna ya kafa, bai samu xore wa ba. Qarancin ma'aikata da farko ya tauye ci gaban wannan shiri, da kuma zanen taswirorin Jihar nan. Amma gwamnati ta yi hovvasa wajen maganin wannan matsala tun da a shekarar 1956, za a ja taswirorin qasashe tsakkanin murabba'in mil dubu ashirin zuwa dubu talatin a shekara mai zuwa.[1]

Haka kuma a game da yaqin nan da shirye-shiryen nan da a ke yi musamman na cututtuka, an matsa qoqarin nan na yaqi da kwaro-kwaro a qasashen bakin kogunan nan, da aikin hana zazzavin cizon sauro wato *malaria* na Sakkwato, da kuma yaqi da irin qudan nan mai jawo ciwon makanta, wato qudan tsando. Ayyukan ciwon barci da na kuturta su ma za a qara buxa su. Haka kuma sabon Asibitin Qashi na Kano ya fara aiki sosai.

gwamnati ce da ta taka rawar gani wajen ba da magunguna da rigafin cituttuka iri-iri a Arewa. A wajen fuskar tarbiyya, ofishin ministan nan, ta mai da hankali musamman wajen matsalar nan ta 'yan Iska a alqaryu, ta hanyar qarfafa hanyoyin wasanni da jam'iyyun kulob na samari musamman. An ci gaba da qara ba da taimakon kuxi ga jam'iyyun taimakon aikin tarbiyya, haka kuma, an taimaka da ba da matuqar goyon baya ga horon nan na *Man o'War Bay*. Ana fata za a sake yin irin wannan Kwas a shekarar 1956 a Jihar Arewa. Ita wannan gwamnati ta haramta zaman banza da aikata masha'a a birni da qauye. Saboda haka kula da tarbiyyar matasa, an bata muhimmanci sosai.

Ta fuskar samar da ruwan sha kuwa, ofishin *Ministan Fidaburdi*, sun yi aikace-aikace da havaka samar da ruwan sha dai-dai gwargwadon qarfin ma'aikatan da su ke da su. An kafa waxansu sabbin makarantun horar da ma'aikata guda biyu. Su ne Ma'aikatar Masu Aikin Famfo a Dikku da ma'aikatar koyon Direba a Kaduna. Ana kuma ci gaba da haqa rijiyoyi cikin hanzari. An kuma haqa rijiyoyi dubu da xari uku, da ramukan rijiyar kwakware guda arba'in da biyar a shekarar 1957. An gina taffuka kusan arba'in waxanda su ke cike da ruwa, a dai-dai wannan lokaci.[2]

A game da hanyoyi kuwa, an sake gina hanyoyi masu yawa, da aka sa masu kwalta a lardin Ilori da na Kaba da Binuwai. A shekarar 1956 aka gaggauta kammala hanyar aiki da mashin, waxanda suka haxa da hanyar Kano-Gumel-Haxeja, da hanyar kwarin Zamfara. A kuma wannan gagarumin shiri, ta haxa da hanyar Kaduna-Kaciya-Kaffi, da hanyar Zariya-Pambeguwa. Ana kuma shirya safiyon hanyoyin Pategi-Egbe, da Kwantagora-Dabai. Cikin manyan ayyukan da aka kammala har da na Kadarkai; waxanda suka haxa da Kadarkon Kogin Kaduna

---

[1] *Kai Da Yanzin Nijeriya*, shafi na 18

[2] *I bid*.

a nan Kaduna, da Kadarkon Kaciya a hanyar Kaduna-Kaffi.[1] Saboda haka Sardauna da majalisarsa basu yi qasa a gwiwa ba wajen ciyar da Arewa gaba don suna da kyawawan manufofi sun kuma nuna misalai ababen koyi da alfahari.

Waxannan kaxan ne daga cikin ayyukan da Sir Ahmadu Bello, ya aikata wajen gina wa da havaka Arewa, saboda yana tsoron kada a bar su a baya har 'yan Kudu su mallake su. Don haka ne kuma ya tsare Arewa don 'yan Arewa. Za a daxe ba a samu gwarzo kamarsa ba wanda ya haxa kyakkyawar niyya da aiki wajen shugabancin al'ummarsa. Ya tsaya tsayin daka wajen kare martabar Sarakuna da kyawawan al'adu da xabi'un Arewa. A zamaninsa ya qarfafa jama'a wajen riqe addininsu na musulunci da Liristanci. Shirinsa na Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, sai ya shagwava 'yan Arewa ya kuma sangarta su, har suka zama ba sa kishin kansu ballanta na Jiharsu, lalaci da rashin qulla fus, sai suka haxu suka yi masu katutu. Saboda rashin shan wahala a harkokin rayuwarsu musamman a zamaninsa. Ya kamata a ce 'yan Arewa sun kaucewa matsaloli biyu da Sardauna ya hango: mallakar 'yan Kudu da maida Arewa koma bayan jihohi a Nijeriya. Amma saboda qaddara ta riga fata, da mutuwar Gamji Xan qwarai, sai al'amuran Arewa suka birkice, har ta kai Arewa ba ta iya dogaro da kanta, abin kuma da ake gudun mata, mallakar 'yan Kudu sai ta haxu da shi.

Duk da cewa an baiwa 'yan Arewa ragamar jagorancin Arewa, amma wannan bai hana ta zama a qarqashin 'yan Kudu ba. A yanzu ana iya cewa, 'yan Kudu na mallakar Arewa takan 'yan Arewa ne kamar yadda Turawa suka mallaki Arewa ta *Indirect Rule*! Don kusan duk manyan ayyuka da harkokin tattalin arziqin wannan qasa na hannun Yarbawa da Ibo ne. Su ne kuma su ke da arziqin sayen hannun jarin ma'aikatu da kamfanonin gwamnati a Nijeriya. Yawan 'yan Arewa a yanzu sai ya zama tarin tsintsiya ne shirim ba shara! Saboda babu wata sana'a muhimmiya da za a ce 'yan Arewa sun riqe kuma tilas ayi da su. Arewa a hannun 'yan Arewa sai ta zama saniyar tatsa ba ga 'yan Kudu ba, har ma tsirarun qabilun Arewa sun yi qarfi, sun kuma yi ilimi da su kuma ake tatsar Arewa.

A manyan garuruwan Arewa da Musulmi suke da yawa kamar Sakkwato da Kano da Katsina da Kaduna da sauransu, ranakun Lahadi na kawo masu cikas wajen harkokin yau da gobe. Saboda a ranar Lahadi Kiristoci ke hutu, su ke rufe ma'aikatu da shaguna da kantunan kasuwancinsu. Don haka sai Musulmi su masu xauki hutun dole saboda harkokin ciniki da saye da sayarwa su kan tsaya ne cak! Wannan babbar illa ce da ke nuna cewa wannan qasaitaccen shiri ya ci tura. Bugu da qari da yawa waxanda aka baiwa ragamar jagorancin Arewa, sun fito sun shaida wa jama'a da bakinsu cewa sun ci amanar Sardauna.

Sardauna ya raja'a wajen ba da ayyuka ba tare da la'akari da cewa yin hakan zai sangarta 'yan Arewa ya kuma cire masu kishin Arewa ba. Ana iya qara kawo

[1] *Kai Da Yanzin Nijeriya*, shafi na 18

wani misali a nan. A shekarar 1958 Sardauna ya qara qaimi wajen aiwatar da shirinsa na qarfafa xaukar 'yan Arewa aiki. A wannan shekara ce Firimiyan Jihar Arewa ya gaya wa taron injiniyoyin larduna na Arewa a garin Kaduna, cewa muhimmin abu game da sha'anin ba da aiki, shi ne a ba da qarfi wajen xaukar 'yan Arewa a makwafin waxanda ba 'yan Arewa ba a manyan muqamai. Ya ce:

"Ba shakka waxanda ke riqe da muqaman tenkibo da akawunan kula da sha'anin ba da aiki sun yi aiki qwarai wajen samun ma'aikata, amma sabbin ma'aikatan da aka xauka suna buqatan taimako daga gare ku."[1]

Sardauna ya ce shi ko yaushe ya *xauki* ofishin *Ministan Fidaburdi* shi ne jigon ci gaban kowace qasa. Saboda haka ne ya sami damar yi masu magana. Ya ce qila sun ji cewa nufin gwamnati ne hanzarta ba da aikin gwamnatin ga 'yan Arewa a kowane aikace-aikace na gwamnati. Wannan magana musamman ta shafi ofishin *Ministan Fidaburdi* wajen ba da aiki da ba da kwangila.[2]

A hankali sai aka cunkusa wa 'yan Arewa son a basu amma ba masu son su nema ba. Saboda nema da qwarewar aiki suna da wahala amma kuma suna qara qwarzanta al'umma su maida ita zaqaquma mai dogaro da kanta. A lokacin da ake shagwava 'yan Arewa ta ba su aiki da muqamai sai suka ci karo kicivis, da ba da kwangila. Da suka ji xadin wannan sana'a sai suka yi watsi da sana'o'i, suka kuma langave wajen neman kwangila, a hankali sai akasarin 'yan Arewa suka zama 'yan kwangila kuma ci ma zaune. Abin takaici kuma shi ne suka zama 'yan kamasho waxanda in an ba su sai su bai wa 'yan Kudu su karvi xan kamashom su soke.

Game da sha'anin ba da kwangila, Firimiya ya ce an sake shirya hukuman Ba Da Tanda ta lardi ta zama Baqar Fata ne "majority" wato mafi yawa. Yin haka zai ya yaye koken da Wakilai da sauran jama'a su ke yi, cewa ba a duba maganar ba da Kwangila ga 'Yan Arewa. Babban abin da za a tuna ko yaushe, shi ne a riqa qarfafa wa xan Kwangila xan Arewa rai, muddin ya yi alqawarin yi wa gwamnati aiki mai kyau. To, da ma abin da 'yan Arewa ke nema ke nan, a sami garavasa ba tare da wahala ba. Kafin ka ce me! Sai ga 'yan Arewa sun zama mabarata masu neman a ba su aiki, a basu muqami ko a basu kwangila don suna 'yan Arewa! Babbar naqasun Arewa shi ne rashin ilimi mai zurfi na jama'a masu yawa ba na tsiraru ba. A hankali kuma sai aka riqa karkatar da shirin Sardauna, wanda yake da kyakkyawar manufa.[3]

---

1 GTK, Ta 849, 16 ga Mayu, 1958, shafi na 1.

2 *Ibid*.

3 *Ibid*.

Ko da yake Sardauna ya zama kamar wani gagara-badau mai renon jama'arsa don ka da su sha wahala yana da manufa wadda yake tafiyarwa. Firimiya ya bayyana cewa;

> *Gwamnatin jiha ne ke shirya manufarta. Ta dogara gare ku da ma'aikata ku tafiyar da manufar. Ba wanda ya yi magana game da manyan shugabannin ma'aikatunku – don kuwa wannan magana ce a cikin 'Yan Arewa har yanzu akwai koke kan ma'aikatan da ke qarqashinku, ciki har da waxansu Turawa da dama da ke muqaman sufetocin Fidaburdi. Saboda aikun ku ne ku sa su bi manufar gwamnati, wadda ko ta halin qaqa dai ita ce uwargidanka. Wannan abu yana cikin ran Ministoci qwarai."*[1] Daga qarshe Firimiya ya ce:
>
> *Na sani daga cikin ma'aikatan fidaburdi Turawa muna da Abokai da dama waxanda suke son Arewa, kuma su ke so su ci gaba da yi wa Arewa aiki. Mun lura kuma da yawa daga cikinsu sun damu game da canje-canjen da qila shirin mulki zai kawo. Ina fata kafin su yanke wata shawara game da halin zamansu nan gaba za su duba takardar da mu ke niyyar gabatarwa ba da daxewa ba. Cikinta za su ga niyyar da mu ke yi na kange masu muqamai na yanzu, da abin da aka shirya wa ma'aikata Turawa da Baqar Fata nan gaba.*[2]

Hakqiqa, Sardauna ya yi duk irin yadda ya kamata shugaba ya yiwa jama'arsa wajen gina su don su tsaya da qafafunsu, su kuma tafi kafaxa da kafaxa da sauran al'ummomi sa'o'insu. Amma sai fatanya ta karye da sauran aiki. Da Sardauna ya rasu, sai shirinsa da manufofinsa suka tafi kabari tare da shi sai dai abin da ba za a rasa ba. Waxanda ya amince za su ci gaba da aikinsa, sai su ka sami wannan dama, suka maida Arewa saniyar tatsarsu ta gado da yawa daga cikinsu kuma suka sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Kudu don son biyan buqatunsu. A halin haka sai 'yan Arewa suka rasa alqibla da madafa saboda sun saba a basu aiki, da muqami da kwangila, amma yanzu duk sun rasa su. Sa'an nan basu da sana'a wajen ilimi kuma sai qaramin sani. A wannan hali sun zama bayiana masu dariya a qasar su ta haihuwa. Su kuma suna ta yiwa Sardauna addu'ar samun Rahama da Aljannah firdausi. Amma abin takaici shi ne sun wofintar da a qidar da ya ba su ta Aiki Da Ibada sun shagalta wajen Bara Da Ibada. Haka Arewa ta zama a hannun 'yan Arewa a wannan zamani a yau.

To, yaya qarshen al'amari yake? Idan 'yan Arewa suka dawo da halayensu na kishi da ikhlasi, za su sami shugabannin da za su kamanta mulki irin nasu

---

[1] GTK, Ta 849, 16 ga Mayu, 1958, shafi na 1.

[2] *Ibid*.

Sardauna wato 'yan Siyasar farko. Idan haka bai samu ba, 'yan Kudu za su riqa yin mulkin gallaza wa 'yan Arewa su qara karya tattalin arziqinsu don su dauwama a mulki su kuma qara maida 'yan Arewa mabarata a Nijeriya. Irin wannan mulki na gasawa 'yan Arewa gurjiya a hannu ne samfurin irin wanda tsohon Shugaban Qasa Cif Olusegun Obasanjo, GCFR, ya yi a shekarun 2003 zuwa 2007. Wata qila azabar irin wannan mulki zai cunkusa wa 'yan Arewa kishin Arewa, ya kuma farkar da su daga barcin da su ke yi, da biris da harkokin rayuwarsu tare da la'akari da matsayinsu a Nijeriya da duniya baki xaya. Daga qarshe idan haka bai samu ba, to, wata qabila za ta taso ta yi qarfi sosai har ta yiwa 'yan Arewa mummunan kisan gillar da zai farkar da su daga barci. Don wannan duniyar ba wata qabilar da zata riqa wa ilimin jama'arta xaukar sakainar kashi ba tare da ta xanxana kuxarta ba. duniya ba za ta tafi da wata al'umma da shugabanninta ke ado da mabarata ba. Saboda duniya ce ta mai qarfi sai Allah Ya isa! wato qarfi wajen ilimi shi ne nagartar al'umma, da kuma qarfi wajen tattalin arziqi na ma'aikata, da kasuwanci da masana'antu. Ai gani ga wane ya isa wane tsoron Allah! Harsashin ci gaban al'umma shi ne riqon addininta da kyawawan al'adu da xabi'u. Domin haka tilas ne Arewa ta yi hattara don ba abin da Dimikuraxiyya ke warwarewa kamar waxannan shika-shikan ci gaban al'umma duniya da lahira. A halin yanzu kar a kuskura amanta da izza da homar da 'yan Kudu ke nuna wa, suna kuma cewa Arewar me? Bata isa ba! Akwai bambancin gasa da hamayya a vangarorin Nijeriya. 'Yan Kudu na gasa da hamayya ne wajen wawason arziqin qasa. Amma 'yan Arewa kuwa na gasa da junansu ne wajen nuna fifikon tara abin duniya.

Dangatakar Kudu da Arewa

Sir Bryan ne ya fahimci dangarkar da ke tsakanin 'yan Arewa da maqwabtanta 'yan Kudu. Su kansu 'yan Kudu da suka rabu kashi biyu: Jihar Gabas da Jihar Yamma basa ga maciji, wataqila saboda manufarsu guda cewadda ta sanya gaba tsaninsu. Ita wannan manufa ita ce ta mallake arziqin wannan qasar. A lokacin da ake kafa sabuwar Nijeriya basu xauki Arewa a matsayin komai bai. A dalilin haka ne ma Sir Bryan ya ce:

> *A wannan lokaci, duk manyan jam'iyyun na Nijeriya, ba wanda ya kula da 'yan Arewa. Ko da suka kafa wannan jam'iyya tasu. Kudu na ganin su kamar 'yan kiyashi ne da za a iya takewa a wuce. 'Yan siyasa na Ibo abokan faxarsu 'yan siyasa na Yarbawa. A ganin su 'yan Arewa, qauyawa, ba su ma isa a yi faxa da su ba. Ibo suka yi ta hawan Yarbawa suna yi musu kaca kaca a cikin jaridarsu Pilot, suna cewa sai sun murqushe wannan jam'iyya ta qabilar Yarbawa. Daga faxa na jaridu, har abu ya fara kai ga faxan ware dantse. Yarbawa suka ga*

abin ba na wasa ba ne, su kuma suka miqe, suka ware nasu dantse. Kowace jam'iyya ta kafa wata jam'iyya ta samarinta a qarqashin 'yan ta kife![1]

Duk sun ware dantse suna faxa da junansu ba domin komai sai don kishin qabila da yankinsu. Ba kuma 'yan ta kife suka kafa ba, a'a har da gina samarinsu da Yammatansu ta hanyar basu ilimi mai zurfi da sana'o'i iri-irin masu kuma daraja domin su taso su mamaye guraben aiki ba a qasashen su ba kawai har ma da Arewa. A cikin shekarar 1955 Jihar Yamma ta fara aiwatar da shirin ilimin Firamare na kowa da kowa. Bayan shekarar biyu sai a shekarar 1957, Jihar Gabas ta xau hannu wajen aiwatar da wannan sabon shiri. Dukkansu sun xauki shirin gina jama'arsu domin kowace jiha ta tsaya da qafafunta ta kuma dogara da kanta wajen samar da qwararran ma'aikata dukkansu kuma suna da burin danne Arewa.

Kafin ka ce kwabo har sun fara kwararowa cikin Arewa domin su cimma wannan buri nasu. Ganin haka fa sai Sir Abubakar Tafawa Valewa ya vara, yana koken cewa:

"Jama'a da yawa suna tunanin cewar Nijeriya qasa xaya ce, amma wannan kuskure ne. Saboda haxin kan wannan qasa a sama yake bai kai har qasa ba, bai wuce ma wannan xakin taron Majalisar Dokoki ba.

A halin yanzu qabilun kudancin wannan qasa wato mutanen Jihar Gabas da Jihar Yamma sai kwararowa suke yi zuwa Arewa, amma ba don su zauna su yi tu'amuli da cuxanya da 'yan Arewa ba, bama sa son yin haka. Mu kuma 'yan Arewa mun xauke su baqi ne da suka zo su mallake mu."[2]

Duk qoqarin da shugabannin Jamhuriyar Farko suka yi don su datse Arewa don 'yan Arewa bai kai ga nasara ba. Saboda qwazo, da kishi, da haxin kan 'yan Jihohin Gabas da Yamma sai da suka maida Arewa akushin tuwo ko kuma wata kasuwa da za a ci kowa ya watse. Wannan ita ce dangartakar Kudu da Arewa.

Nijeriya na da arziqin qasa da na jama'a, a sabuwar Nijeriya, arziqin wannan qasa a Arewa ya fi yawa. Akwai ma'adinai iri-iri da qasar noma mai faxi da albarkar qasa ga ta da gandun daji mai albarka. 'Yan Kudu suna jin tsoron Arewa saboda qarfin arziqin yawan jama'a da albarkar qasa. Sai suka lura idan ba su yi wani abu wajen nakasa tasirin yawan jama'arta ba, to, abadan 'yan Arewa ne za su ci gaba da mulkin Nijeriya in dai tsarin mulkin Dimukuraxiyya Nijeriya za ta bi. Ko da yake Arewa na da matsaloli da yawa amma waxannan matsaloli ba su hana ta ci gaba ba duk da tazarar ilimin boko da Kudu ke taqamar ta yi mata. Har gobe

---

[1] Alhaji (Dr.) Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 52

[2] *The Making of Northern Nigeria*, shafi na 32

Kudu na tsoron yawan jama'ar da Arewa ke da shi da arziqi, tana kuma tsoron tarihinta. Haka kuma haxin kan Arewa wato *Monolithic North* na yiwa 'yan Kudu barazana da tsoratarwa.

Arewa na da tarihin kafa Daular Usumaniyya wadda ta yi suna ta kuma shahara a duniya. A lokacin yaqin Shehu Mujaddadi, Baraden wannan Daula sun kusa su dangane da bakin teku, kafin Turawa su shigo wannan qasa. A wancan lokaci tsoro daga farmakin 'yan jihadi ya razana qasashen kudancin Nijeriya har jini ya zo masu a kaifa. Hankalinsu bai kwanta ba sai da Turawa suka shigo suka basu kariya. Saboda haka 'yan Kudu musamman 'yan Jihar Gabas sai ba tare da vata lokaci ba suka karvi ilimi da addini da kuma al'adun Turawa gaba xayansu. Da suka yi qarfi da qarfin Turawa sai suka xana wa Hausa Fulani waxanda suke su ne Baraden Daular Usumaniyya karan tsana, tun daga wancan zamanin har gobe. Shugabannin Kudu sun qwarzanta jama'arsu da tsoron mallakar Hausa-Fulani wanda suka kira "Hausa-Fulani *Hegemony*", don su ta shi haiqan wajen yaqin kare kansu, im ba haka ba wai za a ci su da yaqin jihadi. Tunda daga wancan lokaci har gobe ba su sassauta wannan mummunan kamfe akan 'yan Arewa ba. Su kuma 'yan Arewa da ake wa wannan mugun shiri sai suka yi biris da wannan abu suka koma masu rawa da bazar 'yan Kudu.

'Yan Kudu saboda iliminsu da wayewar kansu da wayon zaman duniya da qarfin arziqin da suke da shi sai ya rufe masu idon basira har suka zaqe wajen faxa da adawa da kowa, ba sa kuma ganin kowa da mutunci har Turawan Mulki. Don haka sai Turawa suka fahimci 'yan Kudu mutane ne masu butulci masu cizon yatsan da ya ciyar da su. 'Yan Arewa kuma mutane ne masu mutunci da ladabi da biyayya, ga su kuma da kara da karimci. Turawa ba su tsinke da 'yan Arewa ba sai a yaqin duniya na Biyu, a lokacin ne Sarakunan Arewa da jama'arsu suka sadaukar da kawunansu da dukiyoyinsu wajen ganin Ingila ba ta yi qura a gwiwa a wannan yaqi ba. Daga wannan lokaci ne Turawan Mulki suka sallama wa 'yan Arewa suka xauke su Amintattun Abokai abin dogara mara sa butulci.

A dalilin haka sai zumunci mai qarfi ya qullu a tsakanin 'yan Arewa da Turawan Mulki. To, da ganin irin wannan dangartakar tsakanin Turawa da 'yan Arewa fa, sai 'yan Kudu suka kamu da ciwon hassada da baqin ciki, suka riqa zagin 'yan Arewa a jaridunsu suna ce masu ba su da katavus sai yadda Sarakuna da Turawan Mulki suka yi da su. A wancan lokaci Jihar Gabas ke da qarfin arziqi da ma'aikata a ko'ina, sai jam'iyyar NCNC ta fito da siyasar Tsageranci, wadda ke faxa da Turawan Mulki a Kudu, da kuma faxa da Sarakuna a Arewa, saboda mulki takan Sarakuna da Turawa suke yi a Arewa. A wannan lokaci ne idan Sarakuna suka tafi Ikko taro har ihu da halayen iskanci ake yi masu. A wannan lokaci kuwa babu qabilar da ta yi qarfin arziqi da ilimin qabilar Ibo, su ne suka mallake sauran qabilun Nijeriya. Jihar Yamma ma ba a barta a baya ba wajen ilimi da kishin yankinsu. A haka Nijeriya ta riqa tafiya a shagixe, sashe na tsoron

sashe. Henry E. Nwigwe wani xan Jarida ne wanda ya bayyana wasu xalilai da suka kawo qarshen Jamhuriya ta farko, ya rubuta cewa:

"Tun farko mutanen Nijeriya na zama ne a cikin tsoro da firgici. Suna tsoron danniya na wata jiha akan wata saboda babu wani qwaqqwaran dalilin haxin kan jihohi. Girman qasa da danniyar mulkin Arewa suna daga cikin dalilai."[1]

A kullum 'yan Kudu na kururuwar 'yan Arewa za su danne su, amma wannan yaudara ce ta yaqin sunquru wanda 'yan Arewa basu fahimta ba har yanzu. Ko a lokacin da za a kafa sabuwar Nijeriya da 'yan Arewa xari uku (300) aka yi, bayan 'yan Kudu nada zaratan ma'aikata dubbai. Su kansu 'yan Kudu sun san 'yan Arewa ba su da qarfin ma'aikatan da za su mallake Kudu. Saboda haka suke ganin 'yan Arewa kamar kiyashin da za a iya takewa. Amma 'yan Kudu na iya mallakar Arewa baki xaya, kuma abin da suke nema ke nan. Amma sai Arewa ta zama qurungu mugun kifi, kada na ganinka ya kwana da yunwa.

Ko da aka kafa jam'iyyun jamhuriyar Farko, Jihar Gabas da Jihar Yamma basu fito da jam'iyyu da za su raba kan jama'arsu ba, sai Jihar Arewa wadda ga qasaita amma babu haxin kan jama'a. Duk da haka sai da Jam'iyyar NPC ta nuna qwarewa da gogewa a harkokin siyasa da mulki. Nwigwe ya yi nazarin wannan Jamhuriya sosai, ya yi qorafi da cewa:

> *A lokacin da Awolowo yake ganin tasku a zaman waqafin da yake yi a gidan Yarin Calabar, sai Jam'iyyar NPC ta yi wani namijin qoqarin mamaye Jihar Yamma ta amfani da marigayi Cif S.L. Akintola, shugaban Jam'iyyar N.N.D.P. wannan shi ne matakin farko da Sardauna ya xauka na ganin ya samu nasarar mallakar Kudu, wannan wata nasara ce da Jam'iyyarsa za ta riqa yin farin ciki da shi abadan, wanda kuma ya bar Jam'iyyun Kudu cikin baqin ciki da juyayi.*
>
> *A wannan lokaci sai ga Jam'iyyar AG na dushewa da gaggawa a harkokin siyasar wannan jiha; ita kuma N.C.N.C ta kixime har ta rasa samun wata alqibla, tasirinta kuma na matuqar raguwa a kudancin wannan qasa. To, bayan da tura ta kai bango ga Jam'iyyar A.G, sai ga qura ta taso ta dagule wa N.C.N.C, al'amuranta suka dagule har ya zama bata iya taka katavus, im ba a qasashen Ibo da Ikko ba. Wato dai kamar Aradu ce ta faxowa jam'iyyun Kudu, a lokacin da 'yan Arewa*

---

[1] Henry E. Nwigwe, Nigeria: *The Fall of the First Republic*, Mottochild Press, London, shafi na II.

suka yi ma Kudu dirar mikiya, a wannan yunqurin da ya kusan rusa harsashin siyasa a Kudu baki xaya. A wannan lokaci ne Dr. Okpara ya farga, ya yi ta kururuwa baki buxe akan tavarvArewar siyasar wannan yanki, amma ya makara saboda 'yan Arewa sun sami cin galabar siyasa a Kudu qwarai da gaske.

A wannan lokaci ne kuma abutar da ke tsakanin N.C.N.C da A.G ta yi rauni sosai har ta kusa mutuwa kwata-kwata saboda dukkan waxannan Jam'iyyu basa iya tavuka komai, a lokacin da NPC ke ragargaza harsashin siyasarsu.

A cikin wannan hali ne sai ga shirin nan na 'Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa' na bunqasa sosai. Wannan shiri sai ya ci gaba da xaukar ma'aikata baqi musamman Indiyawa da 'yan Pakistan, yana kuma nuna fifikon su akan ma'aikata 'yan Kudu. Ba yadda ba a yi ba don a shawo kan Sardaunan Sakkwato da ya canja ra'ayinsa a kan wannan shiri na Northernisation Policy, amma sai ya qeqasa qasa ya qi.[1]

'Yan Kudu basu ji daxin Jamhuriyar Farko ba ko kaxan saboda tarin iliminsu da bin addinin Nasara da karvar xabi'u da al'adun Turawa sai ba su yi amfani da tasiri kamar yadda suke so ba. Ai wuqar fixar giwa ba girma gare ta ba, sai dai kaifi. To, dama ana tsoron Arewa, ga shi ta farka. Gwanintar siyasa da shugabannin NPC suka nuna ya firgita 'yan Kudu, musamman ganin yadda NPC ta yi amfani da NNDP abokiyar hamayyar AG wajen qoqarin mamaye Jihar Yamma da kuma yadda NCNC ta rasa yin tasiri a wannan jiha kwata-kwata. Ko da yake NCNC ta yi abuta da NEPU, amma wannan abutar bata je ko'ina ba, ballantana ta kawo wa NPC wata cikas a Arewa.

A lokacin da 'yan Arewa ke nuna bajintar siyasa a Kudu, sai kuma ga shirin *Northernisation Policy* na kakkave su daga Arewa. Saboda a rage kaka-gidan da suka yi a wannan qasa. Amma ko kaxan shugabannin Kudu basu xauki waxannan abubuwa da ke faruwa da wasu kamar su sun ci gaba ba don sun maida mugun martani.

Irin waxannan kalamai sun qara assasa shugabannin Kudu xaura yaqin mayarda martanin ga 'yan Jihadi. Idan an kasa kai ga bakin teku, to, su sai sun xauki yaqin mallake wannan qasa tun daga bakin teku har ya zuwa ga sahara. Tunda wannan yaqi, kamar yaqin sunquru ne, yaqi ne na mallake qasa ta hanyar amfani da ilimi da ma'aikata.

---

[1] Henry E. Nwigwe, Nigeria: *The Fall of the First Republic*, Mottochild Press, London, shafi na III

Har ila yau akwai kuma abin da ya qara tsole wa 'yan Kudu ido, wanda shi ne buwayar 'yan Arewa da suka nuna a harkar diplomasiyar qasa da qasa inda suka riqa taka rawar gani kuma rawa mai ban sha'awa a duniya. Saboda haka 'yan Kudu sun nuna mummunan qwanji a kan wanna abu, don haka ne ma, Nwigwe ya ce:

"Nijeriya na fuskantar wahala daga siyasar qasashen waje wato International Politics a qarqashin mulkin marigayi Sir Abubakar Tafawa Valewa. Amma duk da haka sai aka bata matsayi mai daraja saboda an xauka ita ce qasa a Afirka da ke bin tsarin Siyasar Falimantare na mulkin Dimukuraxiyya. Domin aka ne sai aka xauke su tagomashin shugabanni a Afirka. Haka zalika qasar na qasaita sosai ga ta da 'yancin 'yan Jaridu wanda ya fi na kowace qasa a Afirka, ga masu ilimi sai qaruwa suke yi tana kuma da ma'aikata masu qwazo wanda ba kamarsu a wata qasar Afirka.[1]

Nijeriya ta qasaita sosai a qarqashin mulkin Firayim Minista, Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa. Amma wannan shahara wajen mulkin da nuna gwaninta da suna da waxannan shugabanni 'yan Arewa suka yi sai ya jawo masu hassada da qiyayyar mutanen Jihar Gabas, waxanda duk da zurfin iliminsu na zamani sun kasa yin tasiri a harkar siyasa. Haka kuma sun ce hasashe da kalmomin da marigayi Firimiya ke yi sun zama wata babbar barazana ga mutanen Jihar Gabas, wannan sai ya tilasta su xaukar matakan kare kansu daga danniyar 'yan Arewa wanda suka yi qazafin ake son aiwatarwa a qarni na ashirin.

Haka dai Nijeriya ta riqa tafiya tana tangal-tangal a Jamhuriyar Farko, 'yan Arewa na kukan 'yan Kudu za su danne su, su kuma 'yan Kudu na cewa 'yan Arewa ne za su danne su don su mallake Nijeriya. Duk kwarmaton da 'yan Kudu ke yi, da 'yan Arewa xari uku kacal suke fafatawa da xaruruwan ma'aikatan waxannan jihohi guda biyu. Nijeriya ta Arewa ba ta da isassun ma'aikata a Jamhuriya ta Xaya saboda illar Mulkin Mallaka da *Indirect Rule*. To, me zai faru ke nan idan Arewa ta zuba dubban ma'aikata a harkokin wannan qasa?

Sir Ahmadu Bello, Firimiyan Jihar Arewa da Firayim Ministan Nijeriya Sir Abubakar Tafawa Valewa sun yi baqin jini da qaurin suna wajen 'yan Kudu saboda kishin qasarsu, da qaunar jama'arsu da haziqanci da buwayar da suka nuna ba a Nijeriya ba a duniya baki xaya. A dalilin haka ne aka kashe su saboda abin da ke cikin zuciyar 'yan Kudu,"Arewan Me? Bata isa ba." Sai ya fito zahiri. Abin da 'yan Kudu ke san su gani a zamantakewar Nijeriya shi ne Arewa ta zama tabarmar takawa kuma tsummar share majinansu. A ran 15 ga watan Janairun shekarar 1966, Manjo Chukwuma Nzegwu Kaduna ya jagoranci juyin mulkin da ya kashe

[1] Henry E. Nwigwe, Nigeria: *The Fall of the First Republic*, shafi na 1.

manyan shugabannin Arewa, 'yan Jihar Gabas ne da alhakkin wannan kisan gillar babu kuma wanda ya yi mamakin ganin haka. Alhaji Isa Kaita Wazirin Katsina xaya daga cikin manyan Ministocin Sardauna ya ce:

"A ranar Lahadi 17 ga watan Janairun shekarar 1966 na sadu da Manjo Nzeogwu ya kuma shaida mani cewa ya zaman masu tilas su kashe Sardauna saboda shirinsa na Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa', har ya kuma ce: "Ta yaya xan Nijeriya zai zama baqo a qasarsa?"[1]

Wannan juyin mulki ya yi mummunan tasiri a kan 'yan Arewa ba saboda kashe mata manyan mutane da aka yi ba, har ma ya kusan kashe masu kishin Arewa kwata-kwata. Saboda kishin su na jama'arsu da al'adunsu da addininsu ne suka yi shahada. Wannan kisan gillar sai ya sa 'yan Arewa karayar zuci, wani abu na farko a tarihinsu. A dalilin haka sai suka yi birgimar hankaka suka canja hali da ra'ayinsu, a zamantakewar Nijeriya. Suka qi bin koyarwa, 'yan Siyasar Farko na furuci da aiki, saboda tsoron kada su rasa rayukansu irin nasu Sardauna. Matakin farko da suka xauka shi ne na wofintar da shirin Ba 'yan Arewa jan ragama Arewa, saboda son wonzuwa sai suka haxa kai da 'yan Kudu wajen danne 'yan Arewa. A wannan lokaci ne wasu 'yan Arewa suka sayar da Arewa ga 'yan Kudu saboda haka ne aka samu damar illata Arewa. An kuma sami nasara sosai saboda danniyar 'yan Kudu takan 'yan Arewa ne ya talauta wannan qasaitacciyar jiha.

To wane martani 'yan Jihar Yamma suka yi wa Arewa saboda hanqoron mamaye Jiharsu da NPC taso ta yi, a Jamhuriyar Farko? Sir Ahmadu Bello ya qulla wata abuta mai kyau da Firimiyan Jihar Yamma Cif. S.L. Akintola shugaban Jam'iyyar N.N.D.P. Ashe Arewa ta tsokalo tsuliyar dodo ne, da Cif Awolowo ya farkar da jama'arsa sai suka xauki wani shiri wanda ya bambanta da nasu Manjo Nzeogwu, wajen maida martani. Cif Awolowo da jama'arsa sun xauki shirin rusa tasirin Arewa ne a harkar siyasa baki xaya su kuma rusa *Monolithic North* saboda ganin baza su iya mallakarta ba. Saboda Sardauna ne ya haxa kan qabilun Arewa, ya maida su tsintsiya maxaurin ki xaya. To, tunda an kashe Sardauna, ya kuma tafi da kishin Arewa, abu ne mafi sauqi a wargaza haxin kan jama'ar Arewa. 'Yan Kudu sun daxe suna kuka da wannan haxin kai wanda suka kira *Monolithic North*. Amma da Yarbawa suka duqufa wajen jifarsa, da la'anci suna amfani da kafafen watsa labaransu suna aibanta wannan haxin kai, suna kira ga Kiristoci da sauran qananan qabilun Arewa, da su qwaci kansu daga mulkin danniyar Hausa Fulani, saboda lokacin su ya yi, sai ga Haxaxxan Haxin kan Arewa na wargajewa cikin hanzari.

---

[1] Steven A. Amune, *Work and Worship*, shafi na II.

Ba a samu galabar rusa *Monolithic North* sai da aka rarraba kan jama'ar Arewa kashi-kashi: 'Yan *Middle Belt*, da qananan qabilu da Hausa Fulani. Aka kuma raba Arewa zuwa vangarori daban-daban, akwai Arewacin Arewa wanda ake kira "Far-North" ga *Middle Belt* Tsakiyar Arewa sa'an nan ga kudancin Arewa. Da zaratan Cif Awolowo suka xukufa ainun, suna amfani da ilimi da kuxi, da watsa furofaganda sai ga rikice-rikicen addini na varkewa tsakanin Musulmi da Kirista a Arewa. Haka kuma sai ga qananan qabilu na yiwa Hausa Fulani kisan gilla a sassa daban-daban a Arewa. A hankali sai ga Arewa na wargajewa qiyayyar da aka haddasa ta Hausa-Fulani da sauran qabilu sai qaruwa take yi. 'Yan Jihar Yamma sun yi amfani da tarihin Arewa musamman na Daular Usumaniyya wajen cunkusa gaba a zukatan jama'a da niyyar wargaza kan Arewa baki xaya.

A cikin wannan mummunan lokaci ne Alhaji Shehu Usman Shagari, GCFR., Turakin Sakkwato, ya zama Shugaban Qasa a Jamhuriya ta Biyu. Amma shirin Arewan Me? Bata Isa Ba, ta kawo cikas a mulkinsa. Cif Obafemi Awolowo abokin takararsa bai ba shi damar yin ayyukan da Gwamnatinsa ta shirya ba saboda ya yi amfani da zaratansa wajen daqile wannan shiri. Tun daga 1979 har zuwa 1984 Shagari bai sami sukunin mulki ba har sojoji suka hamvare Gwamnatinsa. Duk wata mu'amala da 'yan Kudu za su yi da 'yan Arewa wannan rashin isa suke nuna wa suke kuma aiwatarwa, ba a harkokin mulki ba har ma da na ilimi da kasuwanci da sauran harkokin rayuwa. A duk waxannan wurare kishinsu ya wuce na 'ya'ya da nasaba, don sun fi baiwa kishin 'yanki fiye da na addini muhimmanci qwarai da gaske. Dan haka a zamantakewar Nijeriya, Arewa ce za ta dauwama a cikin qunci da talauci saboda sun fahimci akasarin shugabanninta 'Kaji ne tsaba suke so'. Idan kuma ka watsa masu tsaba sai ka ci karenka ba babbaka.

Idan aka dubi wannan zargin da 'yan Kudu ke wa shugabannin Arewa, sai aga ai biri ya yi kama da mutum. Don a Arewa ne shugabanni ke ado da mabarata da yawa daga cikinsu suna jin daxi suna kuma alfahari da ganin 'yan Arewa, musamman Hausa Fulani sun yi watsi da sana'o'insu sun koma yin bara da tumasanci. Har'ila yau da yawa daga cikinsu na fama da wata irin cutar hauka da ake kira a Turance *Sadism*, mai wannan cuta kuwa ana kiransa *Sadist*. Wannan cuta ce ta qeta. Mai fama da wannan irin cuta yana jin daxi idan ya ga mutane a cikin qunci ko muntukus, ciwo da mayata shi kuma sai ya riqa jin daxi gami da alfahari. A kullum sai tasirinsu da nagartarsu ke dushewa amma alqaryunsu sai bunqasa suke yi da motoci da gine-gine, a wani hali da ya haifar da ruvavviyar al'umma a ginanniyar alqarya.

Saboda haka babu yadda za a yi Mai girma Alhaji Shehu Usman Aliyu Shagari ya samu nasara a mulkinsa saboda rashin madafa. A can Arewa babu kishin Arewa sai kishin 'ya'ya da na nasaba, ga kuma karan tsanar da aka xanawa

Hausa-Fulani. 'Yan Kudu kuma musamman Cif Awolowo, wanda ya so ya shugabanci Nijeriya amma bai samu ba, sai suka tashi haiqan wajen ganin Jamhuriya ta Biyu qarqashin Shugaban Qasa Shagari bata kai labari ba. Haka kuma guguwar siyasar tsageranci samfurin NCNC ita taso daga Arewa ta haxu qiyayyar 'yan Kudu, suka taru suka haifar da juyin mulkin da sojoji suka yi a shekarar 1984, wanda ya dasa aya ga Jamhuriya ta Biyu.

A taqaicen taqaitawa dai, ana iya cewa Jihar Gabas ce ta dasa aya ga Jamhuriyar Farko qarqashin Sir Abubakar ita kuma Jihar Yamma ta dasa aya ga Jamhuriya ta Biyu qarqashin Alhaji Shehu Shagari. Dukkansu suna nuna abu guda ne wato, "Arewan Me? Bata isa ba!" A duk wata dangartakar da Arewa da Kudu a zamantakewar Nijeriya, 'Yan Arewa ne suke cikin qunci da talauci domin sune suka watsar da kishin yankinsu suka koma kishin ya'ya da danginsu, wannan hali ya sa suka sallama wa 'yan Kudu ragamar tatsar Arewa gaba xaya. An maida a Arewa Kidahumar Al'umma a yanzu saboda 'yan Kudu ne malaman makarantu tunda daga Firamare har jami'o'i, su ne Likitoci da jami'an kula da lafiya su ne kuma jami'an Tsaro a Arewa. Babu wata al'umma da za ta sallama waxannan muhimman ayyuka, a waxannan muhimman wurare ga abokan hamayya da maqiya sai 'yan Arewan a wannan zamani. Kuma rashin kishin ne ya haifar da wannan abu. Wata qila, sai an yi masu qisan gilla a wannan qasa don a nuna masu a zahiri 'yan Arewan me? Ba su isa ba! Allah Ya kau da vacin rana. Amma rigakafi ya fi magani. 'Yan Kudu sun qwarewajen iya yaqin sunquru da kisan mummuqe don haka ne suke maida martani ga 'yan Arewa cikin hankali da wayo da dabara. To, ta yaya 'yan Kudu suka sami nasara da galaba a kan Arewa? 'Yan Kudu ba su sami nasarar cimma muradinsu ba sai da aka rusa mulkin Sarakuna a Arewa.

Rusa Muxlaqin Mulkin Sarakuna

Dr. Sani Abubakar Lugga Wazirin Katsina, ya yi tsokaci a kan yadda aka riqa zaizaye mulkin Sarakuna a tsarin mulkin qasa a lokuta daban-daban inda ya yi bayyani, a kan "Sarakuna da Tsarin Mulki." Ya ce:

> *Idan muka dubi yadda Tsarin mulki ya taho, za a gani a zahiri ya taho ne da Sarakuna da masu ilimin zamani da ke tasowa. Amma da tsarin mulkin ya kankama sai masu ilimin zamani wato 'yan boko suka samu yiwa Sarakuna zarra saboda sun sami damar ba da gudunmawar aiki. Amma kuma sai aka yi wa Sarakuna turke da ayyukan En'e da ba da dokoki waxanda Majalisar Sarakuna ta gindaya masu. A dalilin haka ne basu damar ci gaba da yin ayyuka ba. Tsarin Mulkin Richards Richard's Constitution na shekarar 1946 babu*

shakka ya baiwa Sarakunan Arewa muhimmanci tun farko. Amma sai bai yi tasiri sosai ba saboda ya yi baqin jini ga jama'a.

Tsarin mulkin Majalisar Sarakuna wanda ya qunshi kafa dokoki da ba da shawarwari ya sami sauye-sauye masu yawa a tsakanin shekarar 1946 zuwa 1963. Majalisar Sarakuna ta taimaka gaya wajen ci yadda da Arewa gaba, da kuma raya addini da al'adu, da xabi'un jama'a waxanda suka bambanta Arewa suka kuma fifita ta a wannan qasa. Ita wannan Majalisa ta taimaka sosai wajen kawo haxin kan Sarakuna da Shugabanni don su tattauna harkokin mulki, da raya qasa da jin daxin jama'a da kuma shawo kan matsololin da ke fuskantar jama'arsu da masarautunsu. Saboda samar da zaman lafiya da bin doka sun taimaka sosai wajen havaka iko da kwarjinin wannan majalisar.

Wani abin lura shi ne, a lokacin Mulkin Soja a Nijeriya sai ya fito da wasu rukunin masu ilimin zamani guda biyu, ya kuma fifita su wato azuzuwan masu mulki da masu ilimi. Dukkansu kuma sai suka wofintar da Sarakuna. Saboda haka sai waxannan rukunan masu ilimi a Arewa, suka koma suna bin masu Mulkin Soja ko na farar hula. A sabili da haka ne sai aka yi biris da tsarin mulkin Sarakuna da masarautunsu.

Haka-zalika sauye-sauyen da aka samu a tsakanin shekarar 1966 zuwa 1999, musamman tsarin mulkin qananan hukumomi na shekarar 1967 da 1976 ba qaramin raunata mulkin Sarakuna ya yi ba. A shekarar 1976 an kawo tsarin mulkin Qananan Hukumomi ne domin a samar da shugabancin da zai kusanci jama'a wanda zai fi aminci fiye da na gargajiya da aka sani tun fil azal wato mulkin Sarakuna da shugabanni. Haka kuma ana sa ran wannan tsarin Qananan Hukumomi zai kafa harsashin siyasa mai faxi a cikin jama'a. Amma sai gwamnati ta riqa amfani da shugabannin Qananan Hukumomi domin ta daqile tsarin mulkin da take jin zai iya gasa da ita wato mulkin Sarakuna.[1]

Turawan Mulki ne suka kafa harsashin zaizaye mulki da qarfin Sarakunan Arewa. 'Yan Kudu kuma suka xau hannu a wani yaqin martani ga Baraden Daular Usumaniyya waxanda Sarakuna ke wakilta. Ita wannan muhimmiyar Daula ta fidda Arewa ga idon duniya ta kuma bar baya da qura domin maqiya da mahassadan Arewa sun tsorata don haka ne suka xauki matakai na sarari dana

[1] Sani Abubakar Lugga, *Leaders and Conflicts the Role of Traditional Rulers in Security and Conflict Management in Hausa Land*, Nigeria. Lugga Press, Katsina (2004) shafi na . 33-34.

sirri don ganin Arewa bata qara samun damar bunqasa da buwaya a duniya irin wannan ba. A dalilin haka ne Turawa suka xana wa Malamai da Sarakuna karan tsana. Ko da yake Turawan Mulki ne suka kafa Majalisar Sarakuna amma sune kuma suka yi mata talala suka zaizaye qarfin mulkinta domin daga qarshe a turbuxe ta. A shekarar 1966 ne aka kashe wa Arewa Shugabanninta nagartattu wanda ya dasa aya a kan shirin Siyasa da Sarakuna.

Bayan shekaru goma sai sabon tsarin Qananan Hukumomi da aka gabatar a lokacin Shugaban Qasa Janar Olusegun Obasanjo a shekarar 1976 ya illata Majalisar Sarakuna. A lokacin da wannan abu ya faru masu ilimin Arewa da yawa sun yi murna saboda suna ganin wataqila wannan shi ne qarshen yaqin qwatar `yanci da suke gwabzawa tun daga shekarar 1938, a lokacin da COBA ta hudo kai. A wannan shekara ce Turawan Mulki suka cunkusa wa 'yan bokon Arewa qiyayya da hamayya da Sarakunansu. A dalilin haka ne masu ilimin zamani suka xauki yaqi da Sarakuna da taken "yaqin qwatar 'yanci."

Amma shi Shugaba Obasanjo bai karya mulkin Sarakunan Arewa don `yan bokon Arewa su sami dama da galabar samun tarin iko da dukiya ba. A'a, ya karya su ne domin ya aza Jihar Yamma a bisa sauran jihohin Nijeriya, ya kuma kwale wa `yanzuriyar Oduduwa arziqin Nijeriya su warwashe. Bugu da qari ya kuma rusa muxlaqin mulkin Sarakuna ne saboda ya maida martani ga Jihadin Mujaddadi abin da Kudu ke fafitikar yi shekaru aru-aru! Inda Turawa suka tsaya akan wannan yaqi, sai 'yan Kudu su ci gaba har suka kai ga nasara. Haka kuma aka yi, waxanda suke ganin Cif Obasanjo ya taimake su ne da ya rusa masu Sarakuna, to, sai su sake tunani. Ba a sami dammar rusa kan Arewa ba wato *Monolithic North*, sai da aka samu nasarar rusa Sarakuna da zaizayewar mulkinsu. Wannan hali ya haddasa illoli munana a Arewa.

Sir Bryan ne ya ba da labarin cewa, masu ilimin zamani, sun yi dabur suka kafa wata jam'iyya wai ita, *Katsina College Old Boys Association*. Amma da yake ba su da yawa, kuma waxansun su Sarakuna na hararsu, sai halsen wutar ya mace, amma garwashin wutar na nan yana ta ruruwa a qasa.[1] Kamar yadda aka sani ne, ita wannan qungiyar COBA bata a dawa da kowa sai da Sarakuna da `yan Kudu. Amma saboda rashin yawa da suke da shi sai ya zama illa babba ga wannan qungiya.

Ita kwalejin Katsina wadda ta horar da mashahuran `yan Arewa, wadda ta komo Kaduna a cikin shekarar 1938, jimillar xaliban da ta haifa duka duka ba su fi xari uku ba. "To, daga cikin waxannan ya'ya kamar xari uku", in ji Sir Bryan,"nan ne muka sa ido mu sami waxanda za su shugabanci wannan sabuwar Nijeriya.[2] Duk da rashin yawan masu ilimin zamani sai suka taso da son

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 47.

[2] *Ibid*.

shugabancin sabuwar Nijeriya ba da Sarakuna ba. A dalilin haka ne suka kafa yaqin qwatar `yanci, wato yaqi da Sarakuna.

Wanda ya fara kaxa gangar yaqin qwatar `yanci a fili kuwa shi ne Wakilin Bauci, Malam Abubakar Tafawa Valewa a lokacin da Majalisar Wakilai ta yi zamanta na farko a shekarar 1950. Mai Wandon Qarfe ne ya wakilci Cif Kwamishina na Arewa, Sir Eric Thompstone a lokacin da ya tafi hutu. A ranar wannan taro da Majalisar Wakilai ne, Sir Bryan ya ce ya haxu da fishin Abubakar Tafawa Valewa. A wannan rana ce Wakilai suka fara wasan kura da tsarin mulkin En'e, wato Majalisar Sarakuna ta fara samun naushi da tokari. Sir Bryan ya ce, "Ga ni tsugunne bisa kujera, wai ni Cif Kwamishina, suka kama jifa, da suka, da zargi, da halbin tsarin mulkin En'e na lokacin."[1] Ya ci gaba da cewa:

> *Cikin jawabinsa, shi Abubakar Tafawa, da ya kai ga tafasa sosai, sai ya fara al'adan nan tasa, da ya saba yi in ya tafasa. Yana magana yana save hannun riga, ta faxo ya sake savewa. Kamar dai wanda zai kai naushi! A can ya kai ga cewa, "Roqona a yi maza a yi gyara kada a jira sai an ga kawunan mutane suna vingira a lambatu. Ni ba gurina in rushe ba, gurina a gyara zama. Ba za mu karvi a ci gaba da zama yadda ake a yanzu ba . . . Gwamna Lugga, Lord Lugard, shi ya kawo irin wannan samfuri na mulki Indirect Rule. Amma da ya kawo shi, na tabbata, bai yi nufin ya zauna haka ba din din din. Gwamna Lugga ya qarfafa cewa komai za a yi ana saurarawa ra'ayin jama'a. Amma a yanzu, wane ra'ayi a ke saurarawa daga talakawa. Duk wanda ke zaune bisa karagar mulki, lallai, lallai, a sanya shi ya gane cewa shi ne baran jama'a, ba jama'a ne barorinsa ba. Jama'ar nan su ke cishe shi, su ke tufashe shi. Wajibi ne kuwa ya bauta musu akan haka. A ce an bar Sarki ya yi mulki, wahadahu la sharika lahu, babu mai ikon ce masa komi, a sani wannan ya soki hanyar musulunci. Qarhin mulki sai a cire shi daga hannun mutum xaya, a sanya shi ga hannun "Sark Cikin Majalisa." Su kuma 'yan Majalisar a zave su. Kada Sarakuna su ce za su yi zaman doya da manja, da ya'yansu waxanda suka yi makaranta.*[2]

To, abin nema ya samu, bango ya tsage sai qadangare ya shiga. An samu rashin jituwa a fili tsakanin 'yan Majalisar Wakilai da 'yan Majalisar Sarakuna. Ita wannan varaka ita ce ta ragargaza Arewa ta kuma zaizaye qarfinta da tasirinta a Nijeriya tun daga wancan lokaci har ya zuwa yanzu. Saboda abin da Turawan

---

1 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 56

2 *Ibid*.

mulki su ke so su gani shi ne muguwar gaba da hamayya ta yi katutu a tsakanin Sarakuna da masu ilimin zamani don shirinsu na *Divide et impera* ya yi mummunan tasiri a Arewa. A maimaikon Turawan su yiwa waxannan Wakilai nasiha su faxa masu gaskiya, aita yaro kyau take yi bata qarqo, sai suka yi masu angiza mai kantu ruwa. A lokacin da Turawan Mulki ke bin Sarauniya da Gidan Sarautar Ingila sau da qafa suke kuma yin xa'a da biyayya a garesu, a lokacin ne suka koma bayan Wakilai, suka qarfafa masu gwiwa wajen cimma nasara a yaqinsu na gwagwarmayar qwatar 'yanci. Saboda suna son a rusa mulkin Sarakuna. A wannan lokaci babu wanda ya tava tunanin ana amfani ne da masu ilimin zamani don a maida mummunan martani ga Daular Usumaniyya. Saboda a inuwarta tane aka ce Sarakuna suke mulkin kama-karya.

Duk da kangadon 'yan Majalisar Wakilai, sai suka rasa kangado saboda zakwaxin son mulki da muqamin da za su samu, idan suka rusa *muxlaqin* mulkin Sarakunansu. A dalilin haka ne basu lura Sir Bryan da maqarrabansa a kullum masu nuna xa'a, ladabi da biyayya ne ga Sarauniya ba, duk da cewa samfurin Ingila Nijeriya ke bi a tafarkin siyasa. Har-ila-yau basu yi la'akari da 'yan siyasar Jihar Yamma suna zaman lumana ne da Sarakunansu ba saboda a sami haxin kan jama'a mai qarfi da qarko. Amma abin takaici shi ne yadda Wakilai suka shiga saran Sarakunansu, ido rufe, baki buxe ba tare da hangen qarshen al'amari ba. Amma su Turawan Mulki sun hangi wannan rashin kangadon Wakilai zai nakasa Arewa, ko bajima ko ba daxe. A dalilin haka ne ma, Mai Wandon Qarfe ya ce:

> *To, ba girin girin ba dai a yi mai – Kura ta saci ganga. Abin da mutane ke duba ke nan a gare mu. A cikin shirin mulkin Nijeriya ta Arewa, babban abin da kowane xan Arewa mai ilimi ya tsana, shi ne wata daraja muxlaqan wadda mulkin Arewa ya baiwa Sarakuna. Shi ne muka ce da Turanci a ke kira "Sole Native Authority", Ma'anarsa shi ne, cewa doka ta baiwa Sarki muxlaqin mulki, wahadahu la sharika lahu. Ko da shi ke a yadda abin ke tafiya, kowane Sarki yana shawara da majalisa. Amma dai tun da yake doka ta ba shi wannan muxlaqin mulki to bai ya aiki da ita ba, duk da haka ya dai san tsarin mulkin ya ba shi wannan iko.*
>
> *Da aka kawo shawarwari gyaran wannan doka ga majalisar Sarakuna, ran nan an sha daga! Sai da ni, a matsayina na Leftana Gwamna, na tabbatar wa Sarakunan cewa, Ministocin nan ba za su karve musu mulki ba ne. Na ce musu iyakar aikin Ministoci shi ne su shirya yadda aikin zai tafi sosai. Suka ce to in dai har Ministocin nan wakilansu ne kawai to sun yarda da zamansu.*[1]

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 63.

A halin gaskiya kuwa Sir Bryan, zagon-qasa ya yiwa Sarakuna. Don kuwa akwai shirin martani ga Daular Usumaniyya da Turawa ke aiwatarwa a voye. Duk da cewa wannan Gwamna a zahiri yana tare da Sarakuna sun kuma shaqu da shi, amma ai saboda kaza baya hanawa a yankata. Ai yaudara makamin yaqi ne, an kuma yaudari Sarakuna. Saboda Ministocin maimakon su zama wakilan Sarakunansu, masu kuma shirya yadda aikin zai tafi sosai, sai suka karve mulki. A dalilin wannan yaudarar ne 'yan Arewa masu ilimi tare da taimakon Leftana Gwamna Sir Bryan suka yi nasara akan Sarakunansu, a yaqin su na qwatar 'yanci. Daga qarshe muxlaqin mulkin 'yan siyasa sai ya maye gurbin maxlaqin mulkin Sarakuna. Saboda haka sai Arewa ta yi gudun gara, ta faxa zago! Saboda daga wannan lokaci ne yan Kudu kuma suka xauki yaqin maida martani ga Jihadin Mujaddadi. Sarakuna ne kuma wakilan Daular Usumaniyya a wannan zamani. Saboda haka sai a darkake su.

Ko da yake Nijeriya na bin samfurin siyasar Ingila ce, akasarin 'yan Majalisar sun fahimci irin wannan tsarin siyasa na Falimantare wanda yake tafiya kafaxa da kafaxa Sarakuna. Amma sai aka wayi gari 'yan Arewa masu ilimi, waxanda yawansu bai wuce xari uku ba, suke fafitikar neman darkake Sarakunansu, ba tare da hangen illolin da yin hakan zai haifar ba. Malam Abubakar Tafawa Valewa a shekarar 1950 ya nemi a cire qarfin mulki daga mutum xaya, a sanya shi ga hannun "Sarki Cikin Majalisa", a qoqarin da Majalisar Wakilai ke yi na ganin ta rusa muxlaqin mulkin Majalisar Sarakuna. An kuma sami yin haka. To, me ya biyo baya?

A shekarar 1957 sai Malam Abubakar Tafawa Valewa ya rubuto wasiqa ta musamman ga Sir Bryan Sharwood Smith inda ya bayyan masa gajiyawarsa a harkar siyasa. A ran 10 ga Fabrairun shekarar 1957 wato shekara bakwai ke nan da ya kaxa gangar rusa muxlaqin Sarakuna a Majalisar Wakilai, ya rubuta cewa:

Dear Sir Bryan", Ya masoyi Sir Bryan.

Tilas ta sanya in rubuto maka wannan wasiqa, na hangen abin da zai auku gare ni nan gaba. Yanayin qasar Ikko bai dace da lafiyar jikina ba. Ina zaune ne dai kurum, amma ban tava zama cikin farin ciki ba a nan. Ko da shi ke ina sha'awar yin aiki ainun, kuma mutane da yawa suna girmamani. Tunda na shigo nake iyakar koqarina in taimaka ga sanya wannan Tarayya ta Nijeriya cin nasara. Amma ni kaina ban yarda ba da cewar wannan irin Tarayya zai iya tabbata ba da akwai hannun Ingila ba.

A yanzu akwai maganganu da yawa na naxa wazirin Nijeriya, bayan taron shirin mulki, Mutane da yawa kuma suna ta jan sunana a haka. A gaskiya ni ba ni son in zama wazirin Nijeriya indan qasar za

ta zauna ne cikin wannan tsari. Kuma ba ni son in ci gaba da zama a Ikko. Na gaji qwarai da aikin siyasa. Ina tunani ainun na in yi ritaya sululu a qarshen wannan shekara. Ban ga wane aiki ba ne zan kama, don in qara bauta wa Nijeriya ta Arewa. Saboda haka ni ke so in rabu da siyasa ba da wata hayaniya ba. Na sha yin wannan magana da abokan aikina tun tuni, amma sun nuna kamar ba su fahinci wahalce-wahalcen da ni ke ciki ba. Waxansu har su kan ce mani, qiri qiri "Ai sai mutuwa za ta rabaka da Ikko!." To in an aikata abin da nake faxin nan, to zan aikata shi ne ba da saninsu ba . . . Ba wani Ingilishi, Baturen Mulki a qasar nan, wanda ya kai ka saninmu, mu na Arewa. Saboda haka gani na zo gare ka domin . . . Shawara ta ka taimake ni ta yadda wannan rikici na wahalcewahalce nawa na kaina. Ina roqonka kamar yadda xa ke roqon uba.

Nine naka, Abubakar T. Valewa.[1]

To irin wannan tsaka mai wuya da Sir Abubakar ya shiga, irinta ne yawancin shugabannin Arewa ke fuskanta a harkar shugabancin Nijeriya. A duk inda su ka shiga a Ikko hedkwatar Nijeriya, sai su ji kamar an fidda kifi ne a ruwa. Saboda rashin ma'aikata da yalwatar masu ilimi da Arewa ke fuskanta. Amma duk da haka ba safai masu ilimi ke son su faxaxa ilimi da yalwata shi a Arewa ba. Bugu da qari ma su kaxai suke son yin mulki muxlaqan ba tare da Sarakuna ba. Saboda sun fi son mulkin 'yan kaxan masu qarfi, waxanda komai ke hannunsu a Arewa. Illar wannan hali shi ne sai Arewa ta rasa qarfin fuskantar qalubalen shugabancin Nijeriya. Idan shugabannin Arewa suka ta fi Ikko sai ka gansu kamar kwabo a babban aljihun riga. Wato xaixai ku ne kamar furfura akan yaro. Saboda haka sai su kasa taka katavus musamman idan suna da kishin jama'ar Arewa kamar Sir Abubakar Tafawa Valewa. Don kuwa a duk inda suka duba jama'arsu su ke gani a qasa ana takawa!

A lokacin da wannan mashahurin wakilin lardin Bauci ke saran muxlaqin mulkin Sarakuna a Majalisar Wakilai, a shekarun baya, bai tava hangen zai samu kansa a cikin wani hali na kaqa-ni-kayi a harkar mulki ba. Duk da ya san hannu xaya baya xaukar jinka. Sarkin yawa kuma ya fi sarkin qarfi. To, wacce amsa Sir Bryan ya ba shi, don ya karantu a harkar shugabanci? A cikin amsar da ya ba shi a ran 19 ga watan Fabrairu, Sir Bryan ya ce:

Ni da shi ke na yi shekaru da yawa a Arewa na fahince ka, fahinta sosai. Na fahinci dalilan da suka sanya ba za ka iya qara jurewa da zama a Ikko ba, kamar wanda ke zaman murabus. In an

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 90-91.

dubi wata fuska kuma, sai a ga shekarun nan da ka yi a Ikko, ka yi jihadin da ba wani xan Nijeriya da ya yi kamarsa, a wurin bauta wa Arewa da Nijeriya baki xaya. Ka sani, wannan lokaci naka, da ka yi a Ikko, ba lokaci ba ne da ya tafi a banza. Ka sami ilimi, ka sami goguwa irin wadda mutanenka ke buqata. Komai wahala ba za a gafarta maka ba in ka gudu daga gare su. Ka sani, yadda ni na sani, cewa a cikin qasa wadda take yunquri zuwa ga ci gaba, dabarun siyasa, da dabarun yunquri daga cikin 'ya 'yanta su ke fitowa. Tsiron kuma da ya fi kowane tsiro wuyar samu, da wuyar girma, shi ne tsiron shugabanci . . .

Tuna da Pakistan, da qasar Sudan. Pakistan tana gaban Nijeriya da kamar shekarar xari. Sudan kuma suna tsaran juna da Nijeriya. Duba nan kusa da kai a Arewa, ka ga yadda mu ke qarancin shugabanni. In ka kauda waxannan shugabanni da muke da su, sai ka ga mabiyansu, ba su kaisu ba ko kusa.

Wajibi ne Arewa ta riqe 'yan shugabannin da ke gare ta, qan, qan, qan. Wannan ra'ayi nawa zai zaman maka mai karya gwiwa, amma ka sani . . . akwai Abubakar da ya . . .[1]

A matsayin na uba ga duka shugabannin Arewa, ai abin da Sir Bryan kamata ya yi shi ne ya baiwa wannan mashahurin shugaba wannan shawara a shekarun baya, a lokacin da yake saran muxlaqin mulkin Sarakuna ido rufe. A wannan lokaci ne ya kamata ya ce da shi "Tsiron kuma da ya fi kowanne tsiro wuyar samu, da wuyar girma, shi ne tsiron shugabanci" saboda haka sai ka bi sannu. Har-ila-yau ya qara yi masa da nuni da qarancin ma'aikata da Arewa ke fuskanta ainun. Saboda Arewa na vukatar waxannan majalisu biyu: Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai don su riqa aiki tare wajen ciyar da Arewa ne gaba. Amma sai Mai Wandon Qarfe ya qi. Saboda shirin Mulkin Mallaka na rusa Arewa ne ba na havaka ta ba ne. Amma duk da haka wannan misali ya isa ya karantar da 'yan siyasan Arewa darussa masu yawa.

Arewa qarfi take buqata, qarfin masu ilimi da yawa, da siyasa da tattalin arziqi da qarfin Majalisar Sarakuna. Saboda ta na cikin haxari a wannan lokaci har gobe. Arewa jiha ce mai maqiya masu yawan gaske wadda ta taka rawar gani a duniya. Don kuwa a lokacin da ake kafa sabuwar Nijeriya, wasu 'yan Arewa saboda zakwaxin son mulki da wanzuwa sai suka manta da tarihin jihadin Arewa, suka ajiye kansakalin yaqi, a zatonsu 'yan Kudu da qananan qabilun Arewa sun manta ba kuma za su maida martani ba. Amma a lokacin da Arewa ta ajiye yaqin Jihadi a zuwan Turawa, a wannan lokaci ne kuma aka xauki yaqin kai mata mummunan

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 91-92

martani don xaukar fansa, daga cikin Arewa da wajenta baki xaya. A wannan lamari kuma Sir Abubakar ya zama abin nuna misali, don samun darussa akan zamantakewar 'yan Arewa da 'yan Nijeriya.

A duk lokacin da aka yi maganar Jihadin Shehu Mujaddadi sai waxanda ba Musulmi su ji kamar an fama masu ciwo ne. Saboda yadda aka cunkusa masu mummunan ra'ayi akan sa. Sun xauke wannan yaqi, wani kisan gilla ne aka kaiwa waxanda ba Musulmi ba domin a tilasta su shiga musulunci. Saboda haka a kullum neman yadda za su maida martani su ke yi ta kowane hali. Har ila yau masu ilimin Zamani sun nuna rashin kangado da suka xauki yaqi da Sarakunansu wato yaqin kwatar 'yanci, da yaqi da 'yan Kudu wato yaqin qwatar girma a lokaci guda.

A shekarar 1947 aka kira taron Majalisar Dokoki ta Nijeriya, a wannan taro kuma sai Wakilin lardin Bauci M. Abubakar Tafawa Valewa ya zo wannan taro, yana janye da rundunar Arewa ta qwatan girma. Ya fara jawabinsa da murya mai qarfi, yana cewa;

> *Wajibi ne a baiwa jama'ar Arewa da ma su da kansu su shirya mai fisshe su. Kuma wajibi ne a zana iyakacin mulkin Sarakuna. Kowa ya san iyakacin matsayinsa. "Ya karkata murya, a cikin hikima, ya nuna cewa Arewa ba su yarda N.C.N.C. ta wakilci ta ba. Ya ce Arewa mazaje ne, ba su buqatar wani ya yi musu yaqin qwatar girma."Ba mu son mulkin kai yanzu, za mu bixe shi sa'adda komai ya nuna. Ba ga roqon mulkin kai za mu tsaya ba, za mu ma yaqo shi ne, idan lalama ba ta bayar ba.*
>
> *Amma idan Ingilishi suka kuskure, suka fita Nijeriya yanzu yanzu, to mu mutanen Arewa, za mu ci gaba da kabbararmu ta yaqi, muna tafe muna cin qasashen Kudu har sai mun kai Teku, kamar yadda dai muka fara, Turawa suka zo su ka tsare mu." Sir Bryan ya ce, "wannan magana fa, sa'adda Tafawa Valewa ke yin ta, ai sai wanda ke wurin. Kun san a yaqe Fulani, da suka danno daga Arewa zuwa Kudu, mil 150 kawai ya rage musu da su kai Birnin Ikko da ci. Wannan jawabi ya kaxa kowa a cikin Majalisa. Majalisa ta ga abin mamaki, cikin dare xaya ga kwaxon da ba ya cizon kowa zai zama kura. Wannan duk ya faru ina Rezdan na Neja a Mina.*[1]

Ko da yake jawabin Tafawa Valewa ya girgiza Majalisa, ya kuma girgiza 'yan Kudu saboda sun xauki wannan kace-nace na siyasa da mummunar niyya, "muna tafe muna cin qasashen Kudu har sai mun kai Teku", wannan batu ne da suka

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 91-92.

laqabawa suna da "Mafarkin Abubakar Tafawa Valewa." Saboda haka ashe wannan bawan Allah ya tsokalo tsuliyar dodo ne bai sani ba. Domin akwai shirin "Martani ga 'yan jihadin Usumaniyyi aqasa". Tun daga wannan lokaci suka riqa bin sa da bi-ta-da-qulli suka kuma xaura masa talala. Ko da yake wasu sun xauka wata fankama ce ta siyasa marar kima amma duk da haka sai sun datse qarin kunama. Wata qila, wannan ya taimaka wajen quntata masa a zaman sa a Ikko. Amma ko saboda kishin Arewa da Allah Ya sallaxa a zuciyarsa, 'yan Kudu ba za su bar Sir Abubakar ya kai labari ba!

Ina mazajen suke a Arewa? Da ma'aikata da ba su fi xari uku ba, su ne za su yi yaqin Qwatar Girma da 'yan Kudu da ke da gogaggun ma'aikata da su ka fi dubu uku? A bisa hankali da shari'a, shin ya kamata masu ilimin Arewa na wancan zamani su xaura yaqin Kwatar 'Yanci da Yaqin Qwatar Girma duk a lokaci guda? Amma an ce tsuntsun da ya ja ruwa, shi ruwa ka doka! To, me ya faru da Sir Abubakar da haqan 'yan Kudu ya tadda ruwa a yaqin maida martani ga 'yan jihadi? Abdullahi Abba ya ce:

> *...a daren Juma'a 14th Janairun shekarar 1966. Da kamar qarfe biyu na dare wani soja wanda ke kwamandan masu kare shugaban qasa (Federal Guard) mai suna Manjo Okafor wanda yake Abubakar Tafawa Valewa ya shaqu da shi, kuma ya kyautata masa matuqar Kyautatawa, yadda ta kai har iyalan Tafawa sun san shi, ya jagoranci sojojin da suka je suka kame Alhaji Abubakar Tafawa Valewa a gidansa a Ikko. Daga nan suka haxe da wassu 'yan qungiyarsu ta "La'anannu biyar" mai suna Manjo Ifeajuna da sa hannun Ironsi suka kai shi wajen garin Ikko suka kasheshi tare da wani babban Hafsan Soja Fitacce xan Arewa mai suna Birgediya Maimalari da kuma Ministan Kuxi mutumin Jihar Yamma ta tsakiya mai suna Cif Okotie Eboh.*
>
> *Shi Alhaji Abubakar Tafawa Valewa sai suka kai shi wani wuri mai suna Otta wanda ke nisar kaman kilomita arba'in (40) akan hanyar Ikko zuwa Abeokuta suka Lanqaye gawarsa jikin wata itaciya suka qwaqule idandunansa suka sanya fuskarsa tana kallon Kudu. Shi wannan wuri nan ne inda rundunar Musulumci ta Jihadi wanda Shehu Osmanu Xan Fodio ya shugabanta suka tsaya basu qarasa teku ba saboda illan da qudan tsando ya yi wa dawakinsu. Kuma shi kansa Abubakar Tafawa Valewa ya tava tunawa 'yan falli na kudancin Nijeriya a lokacin wata muhawara a majalisar qasa cikin watan Maris zuwa Aprilun shekarar 1947 cewar har wannan lokacin fa Arewa na*

iya qarasa aikin kakaninmu. Da dama ba a fahimci saqon daqe qunshe ga inda aka sami gawar Sir Abubakar ba.[1]

Kisan gillar da aka yiwa Sir Abubakar aka kuma gicciye shi a Otta wani martani ne a zahiri ga 'yan Jihadin Daular Usumaniyya. Kuma aba ce babba ga mai hankali ya hankalta da zamantekewar wannan qasa. Shi kuwa Sir Ahmadu Bello, Manjo Chukuma Nzeogwu ne ya kashe shi a gidansa a Kaduna. Ko da ya hallaka Firimiyan bai voye dalilin yin haka ba. Ya ce sun kashe shi shi ne saboda shirinsa na "Ba 'yan Arewa Jagorancin Arewa" wato *Northenisation Policy*. A farkon shekarar 1966, Arewa ta yi hasarar manyan shugabanni masu yawa da kuma hafsoshin soja da dama. Wannan juyin Mulkin Soja, sai ya maida ci gaban Arewa baya matuqar gaske. Saboda tsoro da fargaba sai ya kuma wasu shugabannin Arewa suka sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Arewa da rahusa.

Qasa mai kyakkyan tarihi irin na Arewa musamman na Jihadin Mujaddadi Usman, ai ya kamata ne, ta yi qarfi sosai a duk tsawon tarihinta saboda waxanda suke da haufin wannan tarihi a shirye suke da su maida martani mummuna ga zuriyar 'yan Jihadi ta kowane hali. A maimakon ta yi haka sai Arewa ta langave ta zama mai dogaro kacokan ga 'yan Kudu ta kowace fuskar rayuwa. Sarakuna da ke baiwa Arewa kwarijini da kariya sai aka sagale su a ragaya a wata fafitikar neman mulki da shugabannin Arewa su ke yi na wajen kafa sabuwar Arewa, da kuma neman Shugabancin Nijeriya. Har yanzu Arewa na fama da illolin mai da Sarakuna qarqashin shugabannin Kananan Hukumomi, a `nasarar' da masu ilimin zamani suke ganin sun samu a yaqinsu na qwatar 'yanci daga Sarakunansu.

Har yanzu waxannan shugabanni na gani akwai nasara tabbatacciya a halin da Arewa ke ciki a yanzu. Wannan ra'ayi ai shucin gizo ne. Saboda haka ne ma har yanzu 'yan Arewa ba su farka ba, suna ta barci har da minshari. Ga abin da Abdullahi Abba, ya ce:

"A nan sai ince kai mai barci ka miqe wata rana kana shirin ganin takaici, kuma ka halaka na bayanka. Babu wani abu sabo a qarqashin rana, abin da ya faru jiya makamancinsa ya tava faruwa shekaranjiya, kuma na iya sake faruwa ko yau ko gobe, sai dai wataqila a sami canjin fuskoki ko kuma nahiya. Allah muna roqonka ka kare mu da karvar cizo biyu a rami xaya."[2]

Idan aka dubi illolin da gaba da hamayya da masu ilimin zamani ke yi da Sarakuna a lokacin kafa sabuwar Nijeriya, sai a ga basu ragu ba, a maimaikon haka ma qaruwa suke yi. Amma 'yan Arewa da yawa basu xauki darussan

---

[1] Abdullahi Abba, *Tarihin Bauchi Ta Yakubu*, shafi na . 63-64

[2] Abdullahi Abba, *Tarihin Bauchi Ta Yakubu*, shafi na 65

abubuwan da suka faru a shekarun baya ba. Matsalolin da ke fuskantar Arewa a sabuwar Nijeriya a yanzu sun ruvanya na shekarun baya da yawan gaske sun kuma fi su haxurra masu munin gaske. Ana iya cewa martani ga 'yan jihadi da Kudu ke yiwa Arewa sai ya xauki sabon salo. A wannan lokaci jama'ar Arewa gaba xayanta ake yaqa, ba shugabaninta ba domin ana ji an gama da su. Sir Bryan ya san da wannan qiyayya mai muni a tsakanin Arewa da Kudu. Ba abin da Kudu ke cewa sai, "Arewan Me?."[1]

A bisa amfani da ilimi, hikima da dabarun zaman duniya, 'yan Kudu na amfani da wasu shugabannin Arewa domin su kassara Jihar da talauci mai munin gaske. Saboda inda talauci ya yi katutu, a nan a ke samun barqewar riqice-rikice da za su hana wannan jiha zaman lafiya tare da ci gaba. A wannan lokaci ne kuma 'yan Kudu ke rera guxa suna cewa talauci ya yi katutu a Arewa! A dalilin haka ne sai aka riqa samun rikice-rikice a tsakanin Musulmi da Musulmi da kuma tsakanin Musulmi da Kirista suna faruwa akai-akai, babu qaqqautawa. To, da aka rusa muxlaqin mulkin Sarakuna sai haxin kan Arewa ya riqa rushewa ta kowace fuska. Wannan ya kawo qarshen buwayar Haxaxxiyar Arewa, *Monolithic North*, ya kuma mai da 'yan Arewa fifa-iya-koma-baya a qasarsu ta haihuwa!

Illolin da rusa Sarakuna ya haddasawa Arewa suna da yawa. A cikin waxanda suka hango zuwan wannan mummunan zamani harda M. Sa'adu Zungur wani katafaren mai ilimi wanda ya shahara a zamaninsa. A wasu baitocin waqarsa, Arewa Jamhuriya ko Mulukiya ya ce:

Niyyar Kudu in suka xaukaka
Duk qasa ta zamo Jamhuriya

Mu dai niyyarmu a karkasa
Don Arewa ta zavi mulukiya

Ku fahimci shiri na Mulukiya
Da yawan haxarin Jamhuriya

Sarki da gidajen shawara
Da shari'a kun ji Mulukiya

Mulki na wakilai gurguzu
Ba Sarki babu Sarauniya

Sai 'yan Sanda, sai Soja, sai

[1] Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 52.

Oda, ita ce Jamhuriya

Fatarmu Arewa ta farga duk
Don ta gane lamarin duniya.[1]

A duk mutanen Arewa a lokacin shigowar Siyasa Arewa babu wanda ya fahimci manufofin 'Yan Kudu kamar Malam Sa'adu Zungur. Domin babu wanda Jam'iyyar NCNC ta ci amanarsa kamar wannan mashahurin Dan-Siyasa. Domin haka ne ya wallafa wannan waqar don ya farkar da Arewa. Ya kuma yi mata fata mai kyau: "Fatarmu Arewa ta farga duk, don ta gane lamarin duniya!"

Ko kaxan tsarin mulkin Mulukiya bai samu tushe a Jihar Gabas ba saboda mulki ne da Sarakuna. 'Yan wannan Jiha kuma ba su da gidan Sarauta na asali. Babu kuma yadda za su bari a kafa wannan mulki saboda zai havaka Arewa. Hajiya Gambo Sawaba, shahararriyar 'Yar Siyasa kuma sananniyar 'Yar NEPU, ta bayyana dalilan da suka sa 'Yan Jihar Gabas musamman 'yan qabilar Ibo zakwaxin son mallake Nijeriya. Amma idan Nijeriya ta zama qasa qarqashin mulkin Mulukiya wannan gagarumin shiri zai ci tura. A dalilin haka, ya zama tilas Nijeriya ta zama Jamhuriya, wanda yake "mulkin Wakilai gurguzu, ba Sarki ba Sarauniya."

Amma idan ana so a mallake Nijeriya, to, ya zama tilas a mallaki 'yan Arewa. Wannan shi ne dalilin abutar NEPU da NCNC. Wataqila ta wannan abutar a varka Arewa! Gambo Sawaba ta bayyana shirin NCNC, da kuma manufar qulla abutar NEPU da NCNC inda ta ce:

> *Malam Aminu Kano a cikin hujjar da ya bayar, na farkon farawa tukuna cewa yayi NCNC suka fara kunno kai, suka kafa jam'iyyar Siyasa a Nijeriya, wanda a wannan lokacin shi kansa Awolowo shi ne sakataren kuxinta, daga baya ya valle ya ce NCNC akwai wani shaihinta, wanda yake Farfesa nasu ne ya ba shi wani sirri. Malaminsa ya fada mashi wannan magana, malamin kuwa shi ne malam Sa'adu Zungur wanda yana cikin mutanen NCNC. NCNC sun ce shaihinsu ya ba su wani sirri cewa a Nijeriya su xinnan, Igbo suna da wata qwaqwalwa, wanda wannan qwaqwalwa tasu idan suka yi qoqari za su mallake Nijeriya, wanda kuma ya samu Nijeriya ya samu West Africa, wanda ya sami Afirka ta Yamma ya sami Africa gaba xaya. Wanda ya sami Afrika ya sami duniya gaba xaya. Wanda ya sami Afrika ya sami duniya gaba xaya. Saboda haka su yi qoqari. Amma fa Nijeriyar nan ba zata samu ba har su kai ga wannan burin nasu sai sun sami 'yan Arewa. To duk mutumin da ya sami Arewa ai*

[1] A.M Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na 354.

shi ya sami Nijeriya wanda kuma ya sami Nijeriya ai ya sami duniya. Wannan ya sa sai suka yi nazari, suka samu waxansu 'yan Arewa a wannan lokacin wanda Sa'adu Zungur shi ne na farko, san nan sai Yahaya Adda, sai Abdulrahman Okene da Abdulrahman na Bida. To, a cikinsu Sa'adu Zungur duk ya fi su haziqanci, kuma ya fi su sannin sirrin abin da NCNC suke ciki. Saboda haka ana cikin wannan hali sai laluran rashin lafiya ya saukar masa, sai ya kira almajirinshi Mallam Aminu Kano ya shaida masa abin da ake ciki "Suna da wani abu aboye na mallakan wannan qasa, don haka ina baka shawara, wannan jam'iyyar NEPU da kake ciki, duk yadda zaku yi ku je ku haxu da su NCNC." Wannan bayani Aminu Kano yayi shi a cikin sirri, domin yanzun ya rigaya ya bayyana. To bayan ya faxa a cikin sirri, aka zo wajen taro inda yake jawo hankalin 'yan NEPU cewan a gane cewa a wannan lokacin, Ibo sun fi kowane qabila na Jihar Kudu yawa. A Nijeriya ta Arewa suna da yawa suna da qarfin zuciya kuma suna da arziqi musamman ma a Kano da Minna.[1]

Malam Sa'adu Zungur ne ya tilasta abutar NEPU da NCNC duk da ya san mummunan niyyar Ibo na mallake qasa baki xaya. Wata qila, a zurfin tunaninsa, yana nufin idan 'yan NEPU suka taimakawa NCNC wajen mallakar Nijeriya, to, za su sami manyan muqamaii. Za su kuma yi amfani da wannan jam'iyya su taimaki Arewa. Malam Zungur yana zaton idan kaza ta qyanqyashe qwan shurwa, to, wannan shurwar ba zata ci kaji ba! Akwai illa a wannan tunani. A zatonsa Arewa za ta samu wani amfani idan NCNC ta kafa gwamnati. Duk da cewa waxannan jam'iyyun siyasa sun karkata akan qabilunsu. Turawan Mulki kuma ba jam'iyyar da suke qi kamar jam'iyyar NCNC. Ita wannan qungiya ta taimaka a fili da a voye wajen rusa mulkin Sarakuna. Domin babu yadda za a mallake Arewa sai fa an rusa mulkin Sarakuna. A dalilin haka ne Shugabannin wannan Jam'iyya suka riqa tunzura 'yan NEPU wajen gaba da hamayya da Sarakunansu.

Saboda haka ba abin da abutar NEPU da NCNC ta haifar sai qarin baqin jini da qiyayya ga 'yan NEPU. A dalilin haka ne NPC wadda Turawan Mulki ke goyawa baya ta xauki yaqin darkake 'yan NEPU a Arewa. An hallaka xaruruwa, an xaure xaruruwa an kuma kassara xaruruwa saboda an zarge su da Siyasar Tsageranci. Firimiya a jawabi da ya yi a rediyo a qarshen shekarar 1954 ya ce: "Babu wanda ya yi mamakin abotar NCNC da NEPU, domin duka jirgi xaya ya xauko su." Rikice-rikicen siyasar da ya harqe a tsakanin jam'iyyar NPC da

---

[1] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*: *Kallabi Tsakanin Qauwuna*, Ganuwa Publishers Zariya, (1993) shafi na . 81 & 82.

jam'iyyar NEPU sun hana Arewa ci gaba har na tsawon lokaci saboda karon bartar da suke yi a tsakaninsu.

Wani abin takaici shi ne da Malam Sa'adu Zungur shi da kansa ya bayyana wa Mr. Awolowo irin mugun shirin da Jam'iyyar NCNC ke da shi, sai shi Awolowo ya sulale ya bar wannan jam'iyya domin ya samawa kansa da jama'arsa 'yanci daga mallakar NCNC. A dalilin haka ne Awolowo ya farkar da Yarbawa akan irin mummunan shirin da NCNC ke da shi. Ayya, shi kuwa Malam Sa'adu Zungur sai ya ingiza kansa da jama'arsa cikin ramin kura. Ya kuma maqalqale wa Dr. Nnamdi Azikiwe, shugaban NCNC wanda ba tare da vata lokaci ba, ya yi amfani da shi ya kuma yi jifa da shi. A lokacin da yake cikin wannan baqin ciki ne, ya wallafa waqarsa ta Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya.

A wancan lokaci da Malam Sa'adu Zungur ya haxa kai da Mr. Obafemi Awolowo shugaban AG da abutar wannan qungiya da NEPU, ta kawo sauqi da ci gaba ga jama'ar Arewa. A wancan lokaci Malam Abba Mai Kwaru ne ya tsaya tsayin daka da sai dai NEPU ta yi abuta da AG amma ba da NCNC ba.[1] Ko da yake bai yi nasara ba amma ya nuna tunani mai kyau da kuma hangen qarshen al'amari. Da ya yi nasara, an qulla abuta tsakanin NEPU da AG da dubban 'yan NEPU da suka sha wahalhalu iri-iri ba su shata ba. Don kuwa da siyasar Tsageranci bata hudo kai a Arewa ba.

Saboda Yarbawa mutanen Jihar Yamma suna da xiyauci da kuma tsohon tarihi, za su fi fahimtar juna da 'yan Arewa fiye da 'yan Jihar Gabas. Haka kuma Yarbawa na da gidajen sarauta da mulkin gargaij wanda ya tasirantu a kan jama'ar wannan yanki shekaru aru-aru kafin zuwan Turawa. Bugu da qari musulunci ya karvu sosai a qasashe masu yawa a Jihar Yamma, akwai kuma taimakekeniya a tsakanin waxannan qasashe da Daular Usumaniyya. Duk waxannan dalilai sun nuna gaya abutar NEPU da AG, za ta fi ta NEPU da NCNC amfani da cimma nasara musamman idan aka yi la'akari da cewa jam'iyyar AG bata da baqin jini gun Turawan mulki da Sarakunan Arewa.

Bugu da qari siyasar AG ta aikine da havaka ilimi da sana'a ce saboda haka sai ta fi dacewa da Arewa. Amma ba siyasar NCNC ba wadda ta kawo siyasar Tsageranci da waqe-waqe tare da kwarmato a bakin kasuwa, amma ba siyasar aiki ba. Saboda haka ba wanda ya yi mamaki yadda NCNC ta jefar da Malam Sa'adu Zungur bayan ta ci amanarsa, a wani irin nuna butulci mai baqantawa.

An ce qaddara ta riga fata. Da qungiyar ko kuma magoya bayan malam Abba Kwaru ne suka yi rinjayi da sun ceci dubban 'yan NEPU ciki harda malam Sa'adu Zungur daga baqin ciki da abutar NEPU da NCNC ta haifar masu. Malam Abba Mai Kwaru ya yi qoqari wajen ceto wannan alamari domin haka ne ya valle daga NEPU, don ya qulla abuta, shi da magoya bayansa sai suka kafa qungiyar NEPO

[1] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*, shafi na 80.

wato *Northern Elements Progressive Organisation*. Shugabannin wannan sabuwar qungiya sune Abba Mai Kwaru da Tanko Yakasai da Gambo Sawaba da kuma Sani Darma. A dalilin haka ne sai NEPO ta qulla abuta da AG ta zama qungiyar NEPO.[1]

Ko da yake rigingimu tsakanin jam'iyyar NPC da NEPU sun daxe suna hana ruwa gudu a Arewa, amma Malam Aminu Kano Shugaban jam'iyyar NEPU mai kishin Arewa ne da kuma son ci gabanta. Yana duban al'amuran siyasarsa da idanun basira, yana kuma xora burinsa na siyasa akan sikelin ci gaban Arewa, amma bai cimma muradinsa na siyasa ba. Wannan mashahurin Xan Siyasa ya farga da cewa maqalkale wa NCNC zai kai Arewa ga hallaka. Alal misali, a lokacin da zave ya zagayo a shekarar 1962, Malam Aminu Kano ya auna siyasar jam'iyyarsa a bisa sikelin ci gaban Arewa. A dalilin haka ne sai ya zartar da hukuncin cewa jam'iyyar NEPU ta janye, kada ta shiga zave. Malam Aminu Kano a matsayinsa na shugaban NEPU, sai ya bada umarnin cewa, "kul, kada wani xan NEPU ya fita jefa quri'a a ko'ina."[2] An sha rubuce-rubuce da maganganu a kan janyewa daga zave da Malam Aminu Kano ya sa NEPU ta yi duk da cewa yin haka zai baiwa NPC galaba. Haka kuma aka yi. Irin wannan siyasa ta nuna kishin ci gaban jiha da al'umma baki xayanta abar koyi ce. Saboda lokaci ya yi da za mu daina siyasar *nafsi-nafsi*, mu kuma ta *ummati-ummati*, wadda ita muka sani akanta kuma muka ginu. Har ila yau rungutsumewar siyasa a Arewa da riqice-rikicen da suke tasowa su turnuqe a tsakanin NEPU da NPC, illar mulki ta kan Sarakuna ne ya haddasa. Shi ne kuma ya taimaka wajen zaizayewar kaifin mulkinsu a Arewa.

Indirect Rule ne ya sanya Sarakuna a matsayi mai haxari domin wannan tsari ne ya sanya Sarki da sarauta a wata aljannar kare, wadda ta raba su da talakawa amma kuma bata basu wata madafa mai qarfi ba wadda zata kare Sarki da sarauta a qarshen *Indirect Rule* ba wato haka aka riqa tafiya dakaka batare da hangen qarshen al'amari ba. Domin a tabbatar da tasirinsu ya zaizaye bayan mulki takan Sarakuna ya zo qarshe sai aka haxa su gaba da 'yan zamani masu ilimi. A qarshen Mulkin Mallaka 'yan siyasa ne suka cimma nasara amma wadda take ba tabbatacciya ba. Domin mulkin Sarakuna a Arewa sai ya zama gwaxayi ba sanka ba ja!

Martani ga Daular Usumaniyya

Akwai wasu dalilai da su taimaka wajen rusa muxlaqin mulkin Sarakuna a Arewa. Waxanda suka taimakawa 'yan siyasa kaiwa ga nasara a yaqinsu na qwatar 'yanci. Na farko, shi ne buwayar Daular Usumaniyya da ta yi suna ba a

---

1 *Ibid*.

2 Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*, shafi na 80.

Nijeriya ba, a duniya baki xaya. Saboda haka ta yi maqiya a ciki da wajen wannan qasa. A lokuta da dama akan nuna cewa baraden wannan Daula sun yi kisan gilla a qasashen da ba na Musulmi ba, domin a tirsasa su karvar Addinin Musulmi. A kuma qarshen wannan Daula an zargi Sarakuna da mulkin kama-karya, da murxiya da zalunci. Saboda haka masu adawa da wannan Daula sai suka riqa cunkusa munanan ra'ayoyi a zukatan 'yan Kudu da qananan qabilun Arewa.

A wajen 'yan Adawa da Daular Usumaniyya, zuwan Turawa sai ya zama rahama gare su. A dalilin haka ne suka xauki Turawa masu ceton su suka kuma rungume su da hannu bibbiyu. Turawan kuma sun fahimci irin zaman doya da manjan da ake yi tsakanin Musulmi da maqwabtansu qananan qabilu. 'Yan Kudu kuma waxanda baraden Usumaniyya suka kai wa farmaki, sai suka shiga gaba mummuna da Sarakuna da masarautunsu. Saboda su ne Tutocin Shehu kuma wakilan wannan Daula a wannan Zamani. Saboda haka sai Sarakuna suka riqa fuskantar gaba da qiyayya daga cikin wannan qasa da wajenta.

An ce ramuwar gayya ta fi ta gayya zafi. Saboda haka qananan qabilu da magoya bayansu 'yan Kudu, sai suka xauki 'yaqin maida martani ga baraden Daular Usmaniya. Sarakuna ne kuma ke wakiltar wannan mashahuriyar Daula a wannan zamani. Ko kaxan 'yan Kudu ba su voye qiyayyarsu ga Sarakuna ba tun daga zamanin Turawa har yanzu. Ko da aka fara kafa qungiyoyin siyasa a Nijeriya, sai qungiyoyin Kudu suka fito da siyasar qabilanci da kishin kare yankin su, sa'an nan kuma suka xana karen-tsana ga *Indirect Rule* wanda suka ce samfurin mulki ne da ya maida Sarakuna kakakin Turawan Mulki, suna kuma masu qiyayya ga shari'ar musulunci da shari'o'in al'ada. Wato dai suna qiyayya ne da duk wani abu da ya shafi Daular Usumaniyya gaba gaxi a fili da a fakaice.

Na biyu, a lokacin da qungiyoyin siyasun Kudu suka kafu akan kishin qabila da yanki, a Arewa kuwa sai kishi ya mutu murus saboda tasirin ilimin da ake baiwa 'yan Arewa, wanda yake yana da bigiren jajmananci na tsarin Hindu, wato Hindu *Caste System*. Saboda haka babu yadda za a sami haxin kan al'ummar da ke wannan tsarin. Don haka ne kishin Arewa bai kankama kamar irin na 'yan Kudu ba. Saboda rashin irin wannan kishi sai 'yan Kudu suka sami galabar farraqa kan Arewa wato suka qarasa abin da Turawan Mulki suka faro. Yaqi da 'yan Jihadi sai ya samu qarfi da goyon bayan qananan qabilu waxanda suka xauki cewa da kurkuku da gidan Sarki duk xaya ne a wajen su.

A hankali su waxannan qabilu suna qarfi wajen ilimi da iko a muqaman gwamnati, Musulmi kuma suna qasqancewa a harkokin ilimi, mulki da sana'a. Da haxin kan 'yan Kudu da goyon bayan qananan qabilu a Arewa, sai aka samu nasarar rusa mulkin Sarakuna wanda kuma abu ne da masu iliminsu ne zakwaxin gani ya auku tun a shekarun baya, a yaqin su na Kwatar 'Yanci daga zamanin COBA.

To, ko da waxannan 'yan Arewa marasa kishin Arewa waxanda kuma rashawar garavasa mai kashe zuciya ta la'anta, suka cimma nasara sai masifu iri-iri suka kewaye Arewa ta ko'ina. An ci nasarar yaqin Qwatar 'Yanci amma samun nasara wajen yaqin qwatar girma sai ya fassakar. A maimakon a samu galaba, sai Arewa ta faxa cikin wani Mulkin Mallakar 'yan Kudu mai quntatawa. A wannan hali da ake ciki a Arewa inda kowa ta kansa yake yi ba ta wani ba. 'Yan Kudu kuma sai guxa da shewa suke yi suna murnar ganin talauci ya yi wa Arewa katutu sa'an nan masifu sun kewayeta ta ko'ina.

Daga qarshe kuma ana iya cewa, 'yan Kudu sun sami damar kai wa ga nasara ne saboda kisan gillar da suka yi wa shugabanni Arewa, masu kishi da qoqarin ganin sun kai ta ga nasara. A cikin shekarun 1939-1959, Sarakunan Arewa sun taimaka gaya wajen havaka dangartakar diplomasiya tsakanin qasar Ingila da qasar Nijeriya ta Arewa. A lokacin Yaqin Duniya na farko da na biyu, Arewa ta tsaya kafaxa da kafaxa da qasar Ingila; ta kuma taimake ta kaiwa ga nasara. Arewa ta yi abubuwan yabo a lokutan ziyarar Mai martaba Sarauniyar Ingila a shekarar 1956 da ta Mai martabar *Duke of Edinburgh* a shekarar 1959, da ta Firayim Ministan Ingila Mr. Harold McMillan a shekarar 1960. An kuma samu ziyarar manyan mutane da dama daga Ingila waxanda suka yaba wa Arewa wajen nuna kara da karimci. A dalilin haka ne Sarakuna da shugabannin Arewa da yawa suka samu lambobin yabo da daraja daga Ingila waxansun kuma suka samu lambobin K.B.E suka zama Sir. Sarkin Musulmi Sir Abubakar shi ne ya sami babbar lambar G.B.E. wanda babu wani xan Arewa da ya tava samun irinta. 'Yan Kudu ba su sami irin waxannan xaukaka da daraja ba. A dalilin haka ne sai suka qara nuna qwanji da qiyayyarsu ga Sarakuna, wakilan Daular Usumaniyya a wannan zamani.

'Yan siyasar Arewa su masun taka rawar gani a tsakanin shekarar 1960 zuwa 1966. A cikin waxannan shekaru Arewa ta qarvi baquncin manyan shugabanin Ingila masu yawa, waxanda suka sami yabo da xaukaka ba ga Ingila ba har ma da sauran qasashen duniya. Siyasar su Sardauna kuwa ta buwaya a Nijeriya har 'yan Kudu na zargin cewa Sardauna zai kafa Daula ne a Nijeriya. Henry E. Nwigwe, ya kawo wannan batu na Daular Sardauna wato "Sardauna's Empire", inda ya ce:

> *Jam'iyyar AG ta faxi a Jihar Yamma sakamakon abun kunyar da ya auku a Majalisar Wakilan wannan Jiha, wanda ya sa aka dakatar da wannan jam'iyya wanda Cif Obafemi Awolowo ke wa jagoranci.*
>
> *Ita kuma jam'iyyar NCNC ta sha fama da wahalhahu da matsaloli iri-iri a Jihar Yamma, a wajen goyon baya da taimakon da ta baiwa Cif Akintola a lokacin da yake adawa da Cif Awolowo, saboda NCNC na zaton idan Cif Akintola ya kada Awolowo to, abutarsa da jam'iyyar NCNC zata xore.*

A maimakon haka, da Cif Akintola ya samu nasara sai ya janye 'yan NCNC da ke majalisar Jihar Yamma ya kafa ta sa jam'iyyar NNDP (Nigeria National Democratic Party). Amma duk 'yan majalisar 27 da ke jam'iyyar AG sai suqa qi bashi haxin kai saboda ganin Akintola yaci amanar shugabansa saboda haka sai suka ga haka baza ta savu ba. Wannan labari sai ya faxo wa wannan jiha kamar aradu daga samaniya.

Bayan 'yan kwanaki, sai Cif Akintola ya qulla abuta da jam'iyyar N.P.C. Wannan abutar ce ta baiwa Sardaunan Sakkwato damar miqa ikon Daular Sardauna zuwa Kudu. Wannan abu kuma sai ya tada hankalin 'yan Nijeriya, wasu kuma masu kishin siyasa suka riqa aibatar wannan hali na Cif Akintola da kuma masifun da ke tafe ga wannan qasa.[1]

'Yan Siyasar Farko na Arewa, sun nuna iko, da hikima wajen aiwatar da siyasar da ta taso daga baya ta turniqe ta kuma kusan mamaye Nijeriya baki xaya. Duk a 'yan shekaru bakwai kacal. A 'yan waxannan shekaru qalilan da samun 'yanci sai ga jam'iyyun AG da NCNC suna cikin ruxu, sun kuma fara murmushewa da dushewa cikin hanzari. A wannan lokaci kuwa Cif Awolowo na xaure a gidan Yari saboda an kama shi da laifin cin amanar qasarsa.

A wata gwanintar siyasa kuma sai NPC ta shiga abuta da NCNC a majalisar Dokoki amma ba a aje ko'ina ba sai ta jefar da ita. A dalilin haka ne ma jam'iyyar NCNC ta koma tana qorafi da NPC amma ba da AG ba abin da aka santa da yi. Nwigwe ya ce xaya daga cikin dalilan da suka sa NCNC ta faxi warwas shi ne akasarin 'yan jam'iyyarta tsofaffin 'yan siyasa ne da masu neman azurta kansu waxanda tunaninsu da ayyukansu basu karvu a Nijeriya ba. Har ila yau Ministoci da 'yan Majalisar Wakilan Tarayyar wannan jam'iyya, suna xauke ne da takardun mambobin jam'iyyun Siyasa guda biyu: xaya na NCNC xaya kuma na NPC.[2] Wato dai Sardauna ya gama da waxannan jam'iyyu ke nan. Saboda haka sai ga Daular Sardauna zata cinye Nijeriya.

Idan aka juyo ga jam'iyyar AG kuma sai aga ita ma a cikin ruxu take, ta kuma rasa karsashi. Har-ila-yau abutar NNDP da NPC ta taimaka gaya wajen dagargaza jam'iyyar AG. A wannan lokaci babu jam'iyya mai qarfin NPC a wannan qasa, Ko da yake ancewannan zato ne na mabiya goyon bayan abutar NNDP da NPC. Don kuwa, a halin gaskiya, mafi yawan 'yan Jihar Yamma ba za su so ganin Daular

---

[1] Henry E. Nwigwe, *Nigeria – The Fall of the First Republic*, shafi na 5-6.

[2] *Ibid*.., shafi na 7

Sardauna ta mamaye qasashen Yarbawa ba.[1] Musamman idan aka yi la'akari da cewa shi wani tauraron Daular Usumaniyya ne da ya taso zai haskaka Nijeriya.

Nwigwe ya ce babu abin da ya sake kawo qulla abutar NCNC da AG kamar tsoron wannan mamaya ta Daular Sardauna ga qasashen su duk da cewa waxannan jam'iyyu ba sa ga maciji amma sai suka wayi gari, tilas su haxa kai su yaqi NPC baki xaya. Wannan tsoro ya zama zahiri saboda ganin abutar da NPC ta qulla da NNDP a Kudu.[2] Ya qara da cewa in ba don an garqame Cif Awolowo a gidan Yari ba, da Sardauna bai sami galabar mamaye qasashen Kudu ba amma duk da haka babu Bayarbe mai kishin kansa da zai so ganin Daular Sardauna ta mamaye qasashen Yarbawa.[3] Bugu da qari Nijeriya a qarqashin shugabancin Firayim Minista Sir Abubakar, ta samu karvuwa sosai ga qasashen duniya musamman qasashen Turai da Amurka. A wannan zamani ne Nijeriya ta zama abar misali a Afirka. A dalilin hakane aka ce:

"Nijeriya ta sha samun yabo daga qasashen duniya a qarqashin shugabancin gwamnatin marigayi Sir Abubakar. A lokacinsa ne aka xauki Nijeriya ce kawai ke aiwatar da mulkin Dimukuraxiyya irin tsarin Falimantare. Wannan qasa kuma na bin tsarin siyasar da ya dace da zamani. Saboda haka aka xauki shugabaninta tagomashin shugabanni a Afirka. Har-ila-yau ita ce qasa wadda tafi kowa ce qasa 'yancin 'yan Jaridu a qasar Baqar Fatan Afirka. Haka kuma tana da yawan jama'a da masu ilimi da yawa. Haka zalika tana da ma'aikata da suka fi na kowace qasa nagarta a Afirka."[4]

Sir Abubakar ya yiwa shugabannin zamaninsa zarra ba a Nijeriya ba, amma a duk faxin nahiyar Afirka. A dalilin haka ne ake masa laqabi da Muryar Afirka wato *Voice of Afirka*. Idan ya yi magana sai duniya ta saurare shi, ta kuma natsu. Saboda mutum ne mai natsuwa da kwarjini da muhibba kusan ace yafi kowa wajen iya lafazi da balaga. Ko da yake ya taimaka gaya wajen ciyar da qasarsa gaba, amma kamar Sardauna sai 'yan jihohin Gabas da Yamma suka yi itifaqi da a kashe shi. Saboda sun xauke shi ne wani barden Daular Sardauna, wadda ta samo asali daga Daular Usumaniyya. Sun kuma kashe shi. Saboda kishin siyasa da addini da qabilanci. Shi Cif Samuel Akintola Firimiyan Jihar Yamma kuma shugaban jam'iyyar NNDP bai tsira ba. An kashe shi.

---

1 *Ibid*.

2 Henry E. Nwigwe, *Nigeria – The Fall of the First Republic*, shafi na 7.

3 *Ibid*. shafi na 6

4 *Ibid*,. shafi na 65

An yi juyin mulkin 15 ga watan Janairun shekarar 1966 bisa tsari da kuma manufa. To, da aka sare kan miciji sai gangar jikin ya mutu. An shirya aiwatar da wannan juyin mulki a bisa matakai ko *Operations* huxu a jere: Yunqurin Damisa, da Yunqurin Kura, da Yunqurin Zaki da Yunqurin Giwa.

Yunqurin Damisa aka aiwatar da farko, a ran 15 ga Janairun shekarar 1966. A wannan yunquri shi ne mafi muni. Waxanda suka aiwatar da shi kuma hafsoshin sojoji 'yan qabilar Ibo ne waxanda suka haxa da Manjo C.I. Anuforo, da Manjo A. A Ademoyega (Bayarbe ne) da Manjo E.A Ifeajuna. Waxannan sojoji su ne suka xauki nauyin kashe manyan shugabanni 'yan Arewa da ke Ikko. A wannan Yunquri kuma Manjo Chukuma Nzeogwu da Kanar Odumegwu Ojukwu da ke Kano, da Leftanan Kanar A.A Madiebo, da Manjo T.C Onwuatuegwu, su ne da alhakkin aiwatar da wannan Yunquri a Kaduna.[1]

A Kaduna 'yan juyin mulkin sun kashe Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato da matarsa da yaronsa Baba Zarumi da wasu Manyan hafsojin soja Yarbawa wato Birgediya Ademulegun da Kanar Shodeinde.[2] Yunqurin Damisa ya cimma nasara amma sauran operations xin basu sami aiwatarwa ba. A Yunqurin Kura, an shirya a kashe wasu Sarakunan Arewa ne har ma an tarasu a Ibadan a ranar 28 ga Yulin shekarar 1966 da sunan taro, sai Allah Ya ba da nasara ga wasu sojoji 'yan Arewa da suka maida martani a ranar 29 ga Yulin shekarar 1966, suka hamvare gwamnatin Ironsi.[3]

Yunqurin Zaki shi ne mataki na uku, wanda a cikinsa ne ake da niyyar kashe sauran Sarakunan Arewa da wasu manyan ma'aikatan Ene-En'e da kuma duka manyan ma'aikatan gwamnatin Arewa da ke dai-dai ko sama da mataimakin sakatare mai xaukar albashin mataki na takwas (GL. 08) a yau. A Yunqurin Giwa ne za a karkasa Nijeriya zuwa gundumomi kowace gunduma kuma a sanya mata kantoma xan qabilar Ibo.[4]

Idan aka yi nazarin Yunqurin Kura, za a ga an so a aiwatar da shi ne don martani ga Jihadin Fulani. Idan aka kashe Sarakuna, a wannan Yunquri za a kashe masarautu ke nan a Arewa. Saboda a kawarda duk wani gugguvin Daular Usumaniyya a wannan zamani, wanda Sarakuna ke wakilta. A Yunqurin Zaki ne qiyayyar 'yan Kudu ga shirin Ba 'yan Arewa jagorancin Arewa, ya fito fili sosai. Idan aka samu damar halaka ma'aikata 'yan Arewa da Sardauna ya gina su a shirinsa na *Northernisation Policy*, to, Arewa za ta koma qarqashin Mulkin

---

1 Abdullahi Abba, *Tarihin Bauchi Ta Yakubu*, shafi na 64

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*

4 *Ibid.*

Mallakar Kudu ke nan da qarfi da yaji. Abin da 'yan Kudu ke zakwaxin son yi shekaru aru-aru.

Yunqurin Giwa kuwa sai ya fito da niyyar da 'yan Kudu musamman 'yan Jihar Gabas ke yi na son mallake Nijeriya baki xaya. A shekarar 1956 jam'iyyar NCNC ta yi namijin qoqarin ganin Nijeriya ta samu 'yancin kai a wannan shekara. Jam'iyyar kuma ta yi niyyar ta wakilci Arewa a wannan gwagwarmayar neman 'yanci amma sai 'yan Siyasan Arewa suka qi shirin suka ce kifi na ganinka mai jar koma! To, idan Jihar Gabas ba zata sami damar mallakar Nijeriya ta fannin siyasa ba, to, sai ta samu da qarfin soja. Amma ta wannan hanyar ma sai shirin yaci tura.

Ko kaxan gazawar Yunqurin Giwa bai hana 'yan Kudu ci gaba da bin wasu hanyoyin mallakar wannan qasa ba. Ana jin an kashe wutar wannan mugun buri amma garwashinta na ta ruruwa. A shekarar 1976 ne wani harshenta ya kama bal!.

Idan aka yi nazarin yadda Arewa take yanzu, ana iya cewa dukkan matakan wannan juyin mulki sun cimma nasara amma ba ta yadda ake so ba. A matakin farko, Yunkurin Damisa ne aka kashe manyan shugabannin Arewa a shekarar 1966. bayan shekarar goma ne sai Shugaban Qasa Olusegun Obasanjo ya aiwatar da Sabon Tsarin Mulkin Qananan Hukumomi a shekarar 1976. A wannan shiri an qirqiro Qananan Hukumomi guda xari uku da biyu (302) tare da gyaran tafiyar da aikace-aikacensu. Ta wannan tsari ne aka aiwatar da Yunqurin Kura da Yunqurin Zaki a fakaice. Don an zaizaye qarfin ikon Sarakuna. Ko ba a samu damar kashe su ba, to, sai a rufe su da ransu abarsu ba sa iya yin komai. Wato a rataye su a ragaya, a bar Sarakuna rai kwakwai, mutu kwakwai.

Haka-zalika, Yunqurin Giwa ma ya kai ga nasara domin yanzu Arewa na qarqashin Mulkin Mallakar 'yan Kudu ne su ne: malamai a Makarantun sakandare da jamio'in Arewa; su ne 'yan Sanda da Sojoji su ne kuma likitoci da jami'an kula da lafiya a duk asibitocin Nijeriya ta Arewa. A harkokin sufuri da kasuwanci kuma, su ne suka saye hannun jarin gwamnati, da bankuna da kamfanoni. A kowane waje na mulki ko kasuwanci a Arewa, 'yan Kudu ne ke cin moriyar wajen. Saboda nasarar aiwatar da Yunqurin Giwa, a fakaice ne yasa 'yan Kudu ke guxar cewa, "Talauci ya yiwa Arewa Katutu"!

Bayan shekara goma da sagale Sarakuna a ragaya a shekarar 1976, a wani martani ga Daular Usumaniyya, sai aka fara yin qorafe-qorafe akan tavarvArewar harkokin 'yan Arewa a Nijeriya. A dalilin haka ne sai aka riqa tuntuvar jama'a ra'ayinsu a bisa matsayin Sarakuna. A wannan lokaci sai a ka kafa wani kwamiti a qarqashin Mr. Samuel J. Cookey a shekarar 1986. Wannan kwamiti ya sami ra'ayoyin jama'a a kan batutuwa kamar haka:

(1) Shafe Sarauta gaba xaya wato ayi watsi da ita; (2) A tsoma sarauta ka'in da na'in cikin hulxoxin gwamnati; (3) A sanya Dimukuraxiyya a cikin tsarin sarauta kamar gwamnatin zamani; (4) A bar sarauta kamar yadda take yanzu; (5)

A sanya talakawa su faxi ra'ayinsu ko sarauta tana da wani tasiri da alaqa rayuwar su.[1]

A wannan zamani sai martani ga Daular Usumaniyya ya xauki wani sabon salo a shekarar 1986. 'Yan Kudu ne alqalan zartar da matsayin Sarakuna da masarautu a Nijeriya, wato maqiyansu ne za su hukunta su. Wannan kwamitin sai ya zayyana bayanan waxannan ra'ayoyi daga qarshe sai ya ba da shawara ga gwamnati kamar haka; (1) Tunda Sarkin Gargajiya wani suna ne da ba a da tabbas kowaye, ya kamata gwamnati ta kafa wata doka da zata zayyana kowaye ta amince a kira shi Sarkin Gargajiya kuma ta ajiye wani kundi da zai qunshi sunayen Sarakunan gargajiya a fuskan doka; (2) A taqaita walwallar waxannan shugabanni a yankin Qaramar Hukuma da kawai suke da tasiri ga al'ummansu. Ko a nan xin ma kada a basu wani aikin yin doka ko aiki Mai martaba ko kuma aikin shari'a.[2]

Gwamnati, ta amince da waxannan shawarwari, a kuma nata ra'ayin cewa ta yi sarautar gargajiya bata da wani tasiri a tsarin rayuwar zamani.[3] A kwai masu goyon bayan wannan ra'ayi har ma wasu kan ce Indiya ta ci gaba ne saboda watsi da gidan sarautar Gargajiya ne. Wannan ba gaskiya ba ne ko kaxan. Qasar Indiya ta kai ga ci gaban masana'antu da arziqi ne bayan ta yiwa tsarin jajmananci karen tsaye daga zamanin Mahatma Ghandi. Saboda watsi da ta yi ne da wannan tsari na *Hindu Caste System* sai likkafarta ta yi gaba. Wancan bigire da Indiya ta jefar, shi Turawa suka afawa Nijeriya ta Arewa ta hanyar ba da ilimin boko. A dalilin haka ne Arewa ta kasa ci gaba, tashin farko kuma da ta yi, sai ya zama tashin gwauran zabo. Har gobe Sarauta nada amfani ga jama'ar Arewa, tana kuma dacewa da kowanne zamani. Qasar Ingila da gidan Sarauta take ci gabanta a wannan zamani.

To, idan sarauta bata da amfani ya Arewa ta kasance bayan an daqile mulkin Sarakuna? Ko kuma mene ne tasirin Yunqurin Kura da Yunqurin Zaki a kan harkokin Arewa a yanzu? Kafin a amsa waxannan tambayoyi sai a fahinci yadda 'yan Kudu suka riqa cin nasara a yaqinsu na martani ga Daular Usumaniyya. A kwai dalilai masu dama da suka taimake su ga kaiwa ga nasara. Na farko dai shi ne ilimin boko da a cunkusa wa 'yan Arewa yana assasa sonkai ne, da rashin tausayin jama'a da son wanzuwa da bautar ya'ya da nasaba saboda yana da bigiren jajmananci. Wannan ilimi ya bambanta da ilimin bokon 'yan Kudu da na qananan qabilun Arewa wanda yake da bigiren Mishan, a dalilin hake masu wannan ilimin ke da kishi da jinqai da taimako. Wannan bambancin tunani da halaye a tsakanin

---

1 Abdullahi Abba, *Tarihin Bauchi Ta Yakubu*, shafi na 45

2 Abdullahi Abba, *Tarihin Bauchi Ta Yakubu*, shafi na 45

3 *Ibid*.

masu ilimin Kudu da Arewa, sai ya haifar da bambancin yaqi a tsakanin 'yan Kudu masu Kishin Yanki da 'yan Arewa masu Kishin Zuriyarsu.

Dalili na biyu kuma shi ne 'yan Kudu suna aiwatar da yaqin Martani da Daular Usumaniyya ne cikin ruwan sanyi, babu kwarmato babu kuma tonon silili. Suna amfani ne da ilimi da hikima da gogewa wajen siyasar qasa da fahimtar siyasar qetare. A cikin wannan tsari ne tsohon Shugaban Qasa Cif Olusegun Obasanjo, wataqila, ya kafa gonarsa a Otta, wato a wajen da aka ce 'yan jihadin Daular Usumaniyya su ka tsaya, a lokacin farmakin da suka kai qasashen Kudu. A kullum wannan gonar tasa, wato "Otta Farm" tana tuna masa ne, qalubalen da ke gaban dukkan mutanen Kudu wato mai da mummunan martani ga zuriyar 'yan Daular Usumaniyya da Sarakuna wakilanta a wannan zamani. Saboda haka tana da muhimmanci a tarihin dangartakar kudanci da Arewacin Nijeriya.

Na uku, 'yan Kudu sai suka riqe ilimi da sana'a da niyyar mallake Arewa da Qasa baki xaya. 'Yan Jihar Yamma suka riqe ilimi na kowane fanni suka kuma yi fice a duniya baki xaya. 'Yan Jihar Gabas suka riqe sana'oi da sufuri da kasuwanci, inda suma suka yi fice a duniya. Abin takaici sai ga Arewa babu ilimi babu sana'a, sai zakwaxin son mulki. A wannan fannin mulki ma 'yan Kudu sun karya sandar mulki da qarfin siyasa tunda suka rusa Haxaxxan kan Arewa wato *Monolithic North*, bayan sun haddasa gaba sun kuma assasa ta a tsakanin Musulmi da Kiristoci mazauna Arewa.

Daga qarshe ana iya cewa 'yan Kudu sun sami galaba da nasara akan Arewa ne saboda sun yiwa 'yan Arewa kyakkyawan fahimta da idon basira. Alal misali, a wani zama da Majalisar Tarayya ta yi, an tafka mahawara akan ba da mulkin Qasa a shekarar 1956. A wannan lokaci Arewa ba ta shirya ba. A dalilin haka sai nan da nan Sardauna ya ce. "Mulkin kai yana yiwuwa a bixe shi kuma a same shi, sa'adda ma'anarsa ta fahintu ga dukkan jama'ar qasa."[1] A wannan lokaci kuwa ko shawartar jama'ar Arewa ba a yi ba.

Wannan kulli kucciya sai ya ba jam'iyyar Action Group da NCNC haushi iyaka, kowa ya tafasa, sai daga qarshe Awolowo ya miqe ya ce: " . . wanxanne jama'a za a ce a koma gida a ji ra'ayinsu. Wane ra'ayi gare su. Su banda ra'ayin bixar abincinsu, da bixar wurin kwanansu, da bixar tufafinsu . . .?" Ya ci gaba har ya ce, "Da qasusuwan Mujaddadi Shehu Usman Xanfodiyo za su ji wannan magana daga bakin xaya daga cikin jikokinsa, da baqin ciki ya sanya qasuwan nan sun girgiza."[2]

Wannan ya nuna tun kafin a sami 'Yancin Kai 'yan Kudu ke da niyya da kuma manufa guda, a yaqinsu na maida martani ga Daular Usumaniyya. A kan wannan manufa guda waxannan jam'iyyun AG da NCNC kan su ya haxe duk da

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 70

[2] *Ibid.*

bambancin da ke tsakaninsu. Tun daga wancan lokaci kuma suka fahimci siyasar 'yan Arewa ba ta wuce ta me zan samu ba? Saboda haka ne basu da wata alqibla, kowa ta kansa yake yi, wajen neman abinci da tufafi da wajen kwana! Ko shakka babu rashin kishi da rashin manufa sun raunana Arewa, sun kuma taimaka wajen wargajewar haxin kanta. A halin da Arewa ta samu kanta a yanzu da wuya Sarakuna da masarauta su yi kwarjini saboda halin kowa ya yi ta kansa da jama'a ke ciki. Amma rusa mulkin Sarakuna da aka yi ya haifarwa Arewa illoli masu yawa da muni.

Illolin Rusa Mulkin Sarakuna

Jihar Arewa ta fil azal, jihace mai bambanci da ban mamaki. Jama'arta kuma shahararru ne. Amma sai ga wannan jiha bayan Mulkin Mallaka ta zama wata irin jiha mai rikici da tashin hankali. A ran 15 ga Janairun shekarar 1966 ne aka kashe so da kishin wannan jiha a zukatan jama'arta. Saboda a wannan rana ce sojoji suka qashe manyan shugabannin wannan jiha, waxanda suka yi suna wajen kishin Arewa. A dalilin haka ne sai wasu 'yan Arewa suka ce, "gani ga wane, ya ishi wane tsoron Allah!" Tun daga wannan rana sai kishin Arewa ya zama nadiri a zukatan shugabanni. Amma gaba da qiyayyar 'yan siyasa da Sarakuna ne suka share fagen wannan juyin mulki, ai sai bango ya tsage qadangare ke samun shiga!

Ita wannan qiyayyarce ta haifar da rashin kishin shugabanni. Wannan rashin kishin jama'ar Arewa ya yiwa Arewa naqasu babba ya kuma taimaka wajen mallakar wannan jiha da 'yan Kudu suka yi. A dalilin haka ne sai Jihar da tayi suna wajen rashin zaman lafiya da lumana ta zama dandalin rikice-rikice da tashin hankali a Nijeriya. A duk inda ake samun rikice-rikice, to, zalunci da rashawa ne suka haddasa su. Waxannan miyagun halaye kuwa su ne suka hudo kai bayan an kashe kishi a zukatan jama'ar Arewa. Saboda haka ne sai kowa ya yi ta kansa. Talakawa basu kishin shugabanninsu. An cunkusa wa da yawa daga cikin su aqidar NEPU saboda haka ai suka shagala wajen faxa da hukuma ba su himmatuwa wajen neman ilimi da sana'a ba. Shugabannin kuma basa kishin talakawansu. A irin halin da Arewa ta shiga ke nan, a wannan qarni na ashirin da xaya, wanda za a ce illolin rusa Majalisar Sarakuna ne ya haddasa su.

Wargajewar haxin kan Arewa sai ya haifar da vullowar masifu iri-iri, waxanda suka qara taimaka wa wajen talautata. Waxannan rikice-rikice sun hudo kai ne da sigar rikice-rikicen addini da qabilanci. Akwai misalai masu yawa amma ga kaxan daga cikinsu.

Akwai misalai da dama da ke nuna Arewa ta zama Dandamalin Hargitsi da Rikice-Rikice musamman na addini da qabilanci. Duk waxannan rikice-rikice da makamantansu su kan haddasa asarar rayuka dubbai da dukiya da kuxaxe waxanda suka fi na biliyoyin nairori. A shekarar 2008 ne aka yi mummunan tashin hankali a tsakanin Musulmi da Kiristoci mazauna garin Jos, wanda ya haddasa asarar dubban rayuka da salwantar dukiyoyi masu tarin yawa. A lokacin

da wannan littafi ke daf da fitowa ne, 'yan Boko Haram suka fito suka gwabza faxa da jami'an tsaro a garin Bauci, da Maiduguri da sauran birane da dama a Arewacin wannan qasa. A kowane lokaci rikici ya varke, abin da gwamnati ke koqarin yi shi ne samar da zaman lafiya a wannan lokaci, ta amfani da qarfin soja wajen kwantar da tarzoma amma bata bincike akan sababin aukuwarsa. Akan yi biris da dalilan da aka gano. Haka kuma bata xaukar qwararan matakai na rigafi, wanda masu hikima suka ce ya fi magani.

'Yan Kudu ba su sassauta yiwa Arewa zagon qasa ta kowanne fanni ba, sai da suka tabbata sun maida ita Dandamalin Rikice-Rikicewaxanda jahilci, da lalaci da zalunci ke haddasawa da assasasawa. A wannan lokaci sun xauka Arewa bata da mafita, tunda yake jama'arta da shugabanninta basu ankara da zangon qasa da kisan mummuqen da 'yan Kudu ke lafta masu ba ballanta na su xauki matakan kariya ko martani. Babu wani amfani da rusa Majalisar Sarakuna ya haifar wa Arewa. A kowanne lokaci sai aga cewa ko da yake an sagale masarautun Arewa a ragaya, tun a shekarar 1976, amma martaba da darajar Sarakuna na nan a zukatan 'yan Arewa. Akwai misali guda masu yawan gaske da za a bayar wanda ya nuna haka.

A ranar 22 ga Afrilun shekarar 1991 sai aka yi tarzoman addini a Bauci sanadin kisan gilla da wasu Kiristoci 'yan qabilar Sayawa suka yi wa xaruruwan Musulmi maza da mata, manya da yara a garin Tafawa Valewa. To da tarzomar ta auku ne a ranar Litinin da dare ranar Laraba 24 ga Afrilun shekarar 1991 lokacin wasu Kiristoci sanye da kayan soja da 'yan Sanda suka faxa cikin gari suka riqa kashe Musulmi a gidajensu banda waxanda ake kamawa anawa aquba a ofishin 'yan Sanda.

Lokacin da jama'a suka ankara sai suka yi gangami suka nufi gidan Sarkin Bauci don shaida masa za su kare kansu. Mutane suka taru mafi yawansu majiya qarfi an ce sun fi mutum dubu goma. Sarkin Bauci shi da kansa ya lallashi jama'a, ya kuma yi jagora tamfar kaza da 'ya 'yanta zuwa gidan Gwamna don shaida masa irin kashe kashen da ke faruwa. Abin da ya auku a Bauci a wannan rana ya nuna wa duk mai hankali cewar a nan Arewa ko a so ko aqi sarauta tana da tasiri. Kuma talaka ya fi girmama ta akan tsarin bature wanda har yanzu bai fahimce shi ba, kuma daman ba a tsara shi don jama'ar Afirka ba. A nan dai ga sarauta tayi wa gwamnati rana.[1]

A kowane lokaci sarauta rana take yi ba dare ba. A wajen yawan qabilu iri-iri mabiya addinin Kirista da Musulmi babu kamar Bauci. Amma Jihar Kaduna ba a baya take ba. Kusan bayan shekara goma da rikice-rikicen addini da ya varke a Bauci, sai irin wannan rikicin addini mafi muni ya vullo a Kaduna a shekarar 2001/2002. A wannan lokaci ne rikicin ya faskara a garin Kaduna, sai kuma

[1] Abdullahi Abba, *Tarihin Bauci Ta Yakubu*, shafi na 46.

Zariya ta yi dabur za ta xauka. Idan Zariya ta xauka, to, sai Kano daga nan wataqila ma rikicin addinin ya mamaye Nijeriya baki xaya. Amma da aka yi amfani da Sarauta sai aka sami galabar kwantar da wannan tarzoma.

Arewa a ko yaushe Jihace mai bambanci da ban mamaki. 'Yan Arewa mutane ne masu muxaukakiyar daraja. Saboda haka suna da mafita a wannan mawuyacin hali da suka sami kansu ciki. Domin Allah (SWT) ba Ya canja wa mutane sai sun canja abin da ke zukatansu. Allah Mai Rahama da Jinqai baya tare gaba ya tare ba, domin haka ne yake ba da sauqi a kowane qunci. 'Yan Arewa za su koma kan karagar iko da xaukaka a wannan qasa, za su kuma iya maida Arewa aljannar duniya idan suka xauqi waxannan matakai.

Komawa ga bin koyarwar addinansu wato musulunci da Kirista tare da nuna tsoron Ubangijinsu ta furuci da aiki. A baiwa Sarakuna da Shugabanni matsayin iko mai daraja wanda ya kuma dace da zamani wato a tsoma sarauta ka'in da na'in cikin harkokin mulkin qasa. Saboda tasirin Sarakuna a kan Jama'a ya fi shekara dubu. Don haka illa ce babba a ce za a share su yanzu don su dai-daita da Jama'ar Kudu, waxanda kamar qabilun Jihar Gabas wayewarsu da xiyaucinsu basu wuce lokacin zuwan Turawa ba. A kuma bai wa ilimin Addinin musulunci darajarsa ba kamar yadda aka xauke shi jeka-nayi-ka, ba kamar yadda Mulkin Mallaka ya maida shi. A riqa baiwa Alarammomi da Shehunan malamai albashi dai-dai gwargwadon da ya dace da albashin masu ilimin zamani; A sauqaqa ilimin boko, a faxaxa shi a kuma yalwata shi kowa ya samu domin a rusa tsarin jajmananci da Turawa suka garqama wa Arewa.

Ilimin Addinin musulunci, ilimi ne mai daraja ba ilimi ne gani-nayi-ka ba, wanda Mulkin Mallaka ya cunkusa mana a zukatanmu. A dai-daita ilimin malamai Alarammomi da ke Tsangayu da mashahuran malamai da ke koyarwa a Zaure don a biya su albashi kamar yadda ake biyan masu ilimin boko. Saboda ilimin Addinin musulunci da ilimin boko duk wajibai ne akan Musulmi xan Arewa. Saboda haka haqqin gwamnati ne ta xauki haqqin ba da su ga kowa ba tare da nuna bambanci ba.

A wajen samar da isassun kuxaxen tafiyar da wannan tsari kuwa sai Jihohi ko Qananan Hukumomi su xauki nauyin tafiyar da karatun Alkur'ani a Tsangayu da makarantun Islamiyya. Su kuma hana waxannan almajirai barace-barace saboda ba su dace da Addinin musulunci da zamani ba. Ya zama wajibi a bambanta almajirai daga miskinai da naqasassu da marasa galihu. Waxannan hukumomi na iya kafa haraji wato `Harajin Allo' a kan kowane Musulmi don a sami isassun kuxaxen ba da ilimin Addinin musulunci ba cikin qunci da talauci ba. Kowane Musulmi zai yi farin cikin biyan naira xari biyar ko naira dubu Harajin Allo a shekara. Don ba wanda zai so ya ga Almajirai cikin qunci da fatara kamar yadda suke a yanzu. Ya zama wajibi a cire abubuwan da muka gada daga Mulkin Mallaka musamman abubuwan da suke tarnaqin hana ci gaba ne!

Ya zama tilas a dawo da aqidar Aiki Da Ibada wanda yake shi ne taken Arewa na asali. Shugabanni su samar da ayyukan yi ga matasa, su kuma tursasa su yin aiki tuquru don ci gaban qasa. Sa'annan su kuma hana lalaci da tumasanci. A kowane vangaren rayuwa a tabbatadda 'yan Arewa ne suke tsaye da qafafunsu dimir-dimir kamar wajen aikin Tsaro, da aikin kula da lafiya da koyarwa a makarantu da makamantansu. A kuma kafa doka da ke nuna laifi ne aga matashi ba shi da sana'ar da ta dace da zamaninsa. Don kuwa rayuwarsa zata zama qwamamawa ga rayuwar xan uwansa mace ko namiji.

Ya kuma zama wajibi a baiwa mata ilimi mai zurfi, a kuma basu damar yin aikin da ya dace da hankali da shari'a domin ciyar da al'ummarsu gaba. A samu kyakkyawar sahalewa a tsakanin Musulmi da Kirista a Arewa. A bar kiran Kirista 'Arne' domin wannan suna na "Pagan" ne, wato mai bin addinin gargajiya ko bautar gunki. A kuma guji yin duk wasu abubuwan da za su kawo rashin jituwa tsakanin zamantakewar Musulmi da Kirista. Don su haxu su yaqi jahilci da talauci waxanda su ne ummul-haba-isin rikice-rikicen a tsakaninsu. Su haxu su yi aiki da taimakekeniya da juna wajen ciyar da Arewa da Nijeriya gaba. Wato a dawo da *Monolithic North* ko Haxaxxiyar Arewa.

A duk lokacin da ake maganar Sarakuna kada a saurari ra'ayin mutanen Jihar Gabas da sauran tsirarun qabilu don akasarinsu basu san martaba da darajar sarauta ba. Kada a manta da gudunmawar Sarakuna wajen gina Arewa da havakarta. A dalilin haka ne aka ce a tsoma Sarakuna ka'in da na'in a cikin harkokin mulkin qasa. Domin Sarakuna 'yan Siyasa ne. Ba kwarjini da muhibbarsu ne 'yan siyasan farko suka taka rawar gani mai ban sha'awa a Nijeriya.

KASHI NA GOMA SHA-UKU

Sarakuna a Siyasa

Kafin a kawo muhimmin gudunmawar Sarakuna a Nijeriya ta Arewa sai a bada labarin Sarkin Musulmi Sir Abubakar wanda Allah Ya qaddara shi zai jagoranci Sarakuna a zamanin mulkin mallaka, da zamanin da Arewa da Nijeriya suka sami 'yanci. Shi ne shugaban Majalisar Sarakuna tun daga shekarar 1060 har ya zuwa qarshe Siyasar farko a 1966.

Sir Abubakar III

Hikimomin Ubangiji suna bada al'ajabi. A lokacin da sauyin zamani zai zo sai Allah cikin hikimarSa ya kawo wasu mutane waxanda za su tafiyar da wannan zamani, Ya kuma yassare musu al'amura ta yadda za su cimma muradinsu. A ranar 15 ga Maris aka haifa wa Malam Usuman xan Sarkin Musulmi Mu'azu (1878-1881) xa wanda ya sanya masa suna Abubakar. A wannan rana ne Turawan Ingilishi suka ci Sakkwato da yaqi suka kuma angije Daular Usumaniyya. A wannan lokaci ne suka kashe Sarkin Muslmi Attahiru I, a Burmi, a ranar Juma'a 27 ga Yuli 1903. Allahu Akbar! Ashe a wannan lokaci da aka kashe Sarkin Musulmi kuma shugaban tsohuwar Daula a lokacin ne kuma aka haifi sabon Sarkin Musulmin sa zai shugabanci sabon zamanin dake tafe. Wato tsohon zamani ya tafi sabon zamani ya zo. Abukakar ya tasi cikin kyakkyawar tarbiyya ta gidan Sarakunan Daular Usumaniyya. Abinka da mai maxaukakiyar daraja, cikin xan qaramin lokaci ya sami ilimin Addini da na zamani masu zurfi. Kakansa ya yi sarautar wannan Daular. Ya kuma tashi a hannun kawunsa Hassan xan Sarkin Musulmi Mu'azu.A lokacin da Sarkin Musulmi Attahiru I ya yi shahada sai aka naxa Sarkin Musulmi Attahiru II. Shi kuma sai ya yi ajali a lokacin da Abubakar ke da shekaru goma sha-biyu da haihuwa. Sarkin Musulmi Muhammadu Mai Turare sai ya hau gadon sarauta (1916-1924). A shekarar 1924 sai Sarkin Musulmi Tambari ya gaji sarauta. Amma bai daxe ba sai aka cire shi a 1931. gwamnan Nijeriya Sir Donald Cameron sai ya naxa Hassan Xan Mu'azu Sarkin Musulmi bayan Sarakunan Karaga (masu naxin sarki) sun gabatar da sunansa, a ranar 24 ga Nuwamba 1931.[1] Kawun Sardauna Abubakar ya zama Sarkin Musulmi.

[1] Jean Boyd da Hamzat M. Maishanu, *Sultan Siddiq Abubakar: Sarkin Musulmi,* Spectrum Books Ltd, Ibadan (1991), shafi na 4.

Ya zama Sardauna

Tun da Sarakuna Karaga (masu zaven sarki) suka zavi Hassan Xan Sarki Mu'azu sarauta sai ya shiga ayyukan ciyar da wannan makekiyar qasarsa gaba. A cikin waxannan sauye-sauye ne ya naxa Abubakar muqamin Sardaunan Sakkwato. Wannan muqami wani matsayi ne babba kuma mai daraja a fadar Sarkin Musulmi. A ranar 30 ga Maris ne Sarkin Musulmi Hassan ya naxa shi wannan sarauta.[1]

Sardauna ke da haqqin kula da 'Yan Sanda da 'Yan Doka da Gidan Yari, saboda haka ba qaramin muqami ba ne. sardauna Abubakar a zamaninsa ya inganta waxannan sashe ya kuma qara wa wannan muqami kwarjini. Yana kuma raka Di'o a duk lokacin da zai kai rangadi waxannan wurare. Muqamin Sardauna ya taimake shi sosai wajen hulxa da Turawan Mulki, 'Yan Sanda da sauran Jami'an Tsaro. Ya kuma tsaya tsayin daka wajen ganin shugabanni na nuna adalci. A kowane mako y akan ziyarci Fursunoni da Gidajen Yari domin ya duba waxanda suka xaukaka qararraki don ya gabatar wa Alqalin Alqalai. Wanda shi kuma zai gabatar da su gaban Di'o.[2]

Ta haka ne zai tabbatar ana aikata adalci da kula da waxannan muhimman wuraren.

A cikin shekarar 1934 Sarkin Musulmi Hassan Xan Mu'azu da Sarkin Gwandu Usuman da Sarkin Kano Abdullahi Bayero tare da Sardaunan Sakkwato Abubakar suka tafi Ingila ta jirgin ruwa mai suna SS Appam.[3]

Ya samu qwarewa da horo wajen ayyukansa. Saboda haka sai ya goge a wajen hulxa da jama'a da Jami'an Mulki, saboda haka sai likkafarsa ke qara ci gaba. A watan Febrairun shekarar 1938 aka naxa shi Hakimin Talatar Mafara.

Ya Zama Sarkin Musulmi

A ranar 31 ga Mayun shekarar 1938 ne Sarkin Musulmi Hassan ya yi ajali, Sarakunan Karaga, bayan zamansu ba su vata lokaci ba sai Waziri ya bayar da sunan Sardauna Abubakar. A wannan shekarar aka naxa Sarkin Musulmi bisa cancanta da dacewa. Shi ne ya zama masillar xinke Arewa da Nijeriya baki xaya. Sarkin Musulmi Abubakar III yana hawa gado sai ya xauki sarautar nan tasa mai daraja ta Sardauna ya naxa wa xan'uwansa, Ahmadu Hakimin Ravah, wanda shi ma ya shiga takarar neman Sarkin Musulmi. Da wannan muqami na Sardaunan Sakkwato ne ya riqa shahara har ya zama Firimiyan Arewa a 1954.

Sarkin Musulmi Abubakar III ya fuskanci qalubale iri-iri a zamanin mulkinsa.

---

1 Jean Boyd da Hamzat M. Maishanu, *Sultan Siddiq Abubakar, shafi na 15.*

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*, shafi na 6.

Yana hawa karagar mulki sai yaqin Duniya na Biyu ya varke a 1939. a watan Janairu na wannan shekara ya yi shirin qaddamar da wata Jarida wadda aka kafa don ta taimaka wajen yaxa labaru da furofagandar yaqi. A wannan lokaci ne kuma Rupert East da Abubakar Imam suka tafi shaida masa dalilin kafa wannan Jaridar wadda ita ce 'Faxin Gaskiya', kuxinta kuma kwabo xaya! Sai Sarkin Musulmi ya amsa da cewa, 'A, ai gaskiya ta fi kwabo!'[1] Wannan amsar sai ta zama raxin sunan wannan Jarida; 'Gaskiya Ta Fi Kwabo'. Sarkin Musulmi Abubakar III ke nan ya sanya mata suna, ya kuma albarkace ta har ta zama wata mashahuriyar Jarida a Nijeriya da maqwabtanta.

Sarkin Musulmi Sir Abubakar Saddiq, Sadauki ne wanda Allah Ya baiwa kuzari, qarfin hali, adalci tare da haqurin zama da mutane. Ya Allah kuma Ya albarkace shi da lafiya da tsawon rai. Don kuwa kusan a kullum a kan hanya yake a bisa mota, jirgin qasa ko jirgin sama wajen tafiyar da ayyukan jama'arsa. Wani lokaci idan mutum ya dubi irin yadda yake halartar bukukuwa iri-iri da aka gayyace shi a kuma wurare daban-daban masu nisan gaske, sai mutum ya tambaya, ya ce, "Yaushe ne Sarkin Muslmi ke samun lokacin hutu?"

A wajen harkar shugabanci kuwa shi Sarki ne, Sakaina mai iya ruwa! Sir Abubakar ya qware wajen hulxa da Turawan Mulki, wajen jagorancin Sarakunansa tare da tafiya da 'yan siyasa da sojoji a lokuta daban-daban. Sarki ne kuma da ya sami amincewar qabilu da mabiyan addinin Kirista da arna. Duk jama'arsa ce, ya kuma riqe su da zuciya xaya bisa adalci. Don haka qasar baki xayanta ta riqe shi a matsayin wani Uban Qasa mai faxa a ji.

Da shi aka yi gwagwarmayar neman 'Yancin Qasa. Da shi kuma aka karvi wannan 'yancin a shekarar 1960. a matsayinsa na Uban al'ummar Nijeriya baki xaya ya taimaka gaya wajen renonta ya kuma xinke varakarta sau tari. A dalilin haka ne ya sami lambobin girmamawa da na yabo masu yawan gaske, tun daga zamanin Turawan Mulki har ya zuwa Jamhuriya ta biyu da Mulkin Soja. Turawan Mulki sun tsinke da irin sadaukantaka da gwanintarsa wajen mulki da hulxa da jama'a, don haka ne Mai martaba Sarauniya Elizabeth II ta ba shi lambobin girmamawa masu yawa a lokuta daban-daban kamar: M.B.E., C.M.G., K.B.E. Shi ne xan Nijeriya na farko da Mai martaba ta baiwa lambar G.B.E. Sir Bryan Sharwood Smith ya liqa masa ita a watan Yulin shekarar 1954. har yanzu kuma babu wanda aka baiwa irin wannan lambar.

Sarakunan Arewa sun ginu ne a kan qa'idojin mulki da shugabannin Daular Usumaniyya suka shimfixa da kuma qarin litattafai a kan Siyasa suka rubuta. Har'ila yau a zamanin Sarkin Kano na goma sha-bakwai Muhammadu Rumfa xan Abdullahi Burja (1463-1499) ya gayyaci Imam Almaghili a lokacin yana ziyartar Katsina zamanin sarautar Sarki Muhammadu Korau da ya zo Kano ya bada

[1] Jean Boyd da Hamzat M. Maishanu, *Sultan Siddiq Abubakar*, shafi na 15.

gudunmawarsa. A wajen shekarar 1494 Imam Almaghili ya zo Kano inda ya taimaka wa Sarki da Litattafai a kan mulki, *Taj Ad-Din Fima Yajuz Alal Hukkam*. Waxannan litattafai sun taimaka wa Sarakuna wajen fahimtar mulki da gogewa a kansa. Saboda haka tun kafin Turawa su shigo Arewa, Sarakuna sun san qa'idojin Siyasa.

Qa'idojin Siyasa

Sarakuna 'yan siyasa ne, amma siyasa tabbataciya, wadda ta samo salsala daga Shehu Abdullahi Gwandu qanin Mujaddadi da Sarkin Musulmi Muhammadu Bello, xan Shehu Usmanu xan fodiyo. Sarki Bello shi ne halifa na biyu ga Daular Usmaniya, wadda ita ce tushen Mulkin Sarakuna a Arewa. Wannan mashahurin Sarki kuma malami matafannani, wanda a zamaninsa ya karanta littattafai daban-daban da suka kai dubu ashirin.[1] Ya qware sosai a harkokin siyasa, a inda ya samu yabo daga mahaifinsa Shehu xan Fodiyo, wanda a cikin littafinsa mai suna *Najmul-Ikhwani*, a inda Mujaddadi ya ce: "Ku shagaltu da karatun littafan da xana Muhammadu Bello ya rubuta. Saboda ya kasance mai zurfin ilimi ne ga tarihin musulunci kuma mai bincike ne ga harkokin siyasa matuqar bincike."[2]

Sarki Muhammadu Bello, ya wallafa littattafai da yawa game da siyasa, waxanda suka taimakawa Sarakuna da shugabannin wannan qasa da sauran qasashen duniya akan harkokin mulki. A cikin waxannan littattafai masu muhimmancin gaske, akwai: *Alqawa'idut Tabsiri Lissiyasati* da *Gaisul Wabli fi Siratil Imamil Adali*, da kuma *Usulus Siyasati*. A dalilin roqo na musamman da Sarkin Katsina Umarun Dallaje ya yi ne, sai Sarkin Musulmi Bello ya rubuta *Usulussiyasati*, wanda ya taimaka gaya wajen kafa tabbatacciyar siyasa a Arewa, a wancan zamani. Ya kuma taimaka wajen horar da siyasa ga 'yan Arewa har suka shahara a wannan fanni.

A cikin wannan littafi, Bello ya fayyacewa Sarakuna da kuma shugabanni haxarori da fa'idodin da ke cikin shugabanci. Shugabanci, abu ne mai wuya da haxarin gaske, saboda akwai qwayar zalunci, a qoqon zuciyar xan-Adam. Domin haka ne sai zalunci ya zama kamar ciwo, wanda ba shi da magani sai tsoron Allah ke sa aikata adalci. Saboda haka tabbatacciyar siyasa, ita cewadda ta kau da zalunci ta kuma kafa adalci a shugabanci. Dalilin haka ne wannan littafi *Usulus Siyasati* yake da amfani ba a lokacin Daular Usumaniya, har gobe. Saboda littafi ne da zai zama wata babbar madogara ga shugabannin wannan zamani, ya kamata a yi bitar sharhin wannan littafi.

Sarakunan Arewa sun ginu ne akan tushen da Shehu Mujaddadi ya kafa masu, sun kuma karantu da littattafai a kan shugabanci da siyasa musamman mashahurin

---

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi Ta Jihar Sakkwato Na Xaya* (June 1983), shafi na 80

[2] *Ibid.*

littafin nan *Liya'ul Hukuma* na Shehu Abdullahi xan Fodiyo da littafin *Usulus Siyasati*, wanda ake bayani a kansa a yanzu, wanda malam Muhammadu Isa Talatar Mafara, ya taqaita, ya kuma fassarashi.[1] Wannan liffafi ya bayyan qa'idojin siyasa waxanda suka taimaka wa Sarakunan Arewa a wajen tafiyar da sha'anin mulkin Arewa.

Wannan littafi *Usulus Siyasati* sai kamar ya fi dacewa da wannan zamani na mu na mulkin siyasa, kuma mulki irin wanda duniyake ya yi. Ko mutum bai samu lttafin ba, zai amfana sosai da sharshin wannan littafi. Muhammadu Bello, ya fara rubuta littafin:

"Da sunan Allah Mai-jinqai, Mai-tausayi. Bawa, talaka mai-buqata ga rahamar Ubangijinsa, Muhammadu dan Usmanu wanda aka fi sanin sa da sunan Bello ya ce: "godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya yi mana baiwar Imani da musulunci. Ya kuma shiryar da mu ta hanyar shugabanmu kuma majivincin al'amarinmu wato Annabi Muhammadu, Mafificiyar tsira da Maxaukakiyar gaisuwa daga Maxaukakin Sarki Allah su tabbata a gare shi."

Bayan haka sai Muhammadu Bello ya ci gaba da ambata dalilan da suka ja shi ga ya rubuta wannan littafi. Dalilin kuwa shi ne roqon da Umarun Dallaje Sarkin Katsina na wancan lokaci ya yi a gare shi. Bello ya ce:

"Dan'uwa, mai tausayi, amintacce mai gaskiya Umaru Dallaje, mutum mai qoqari gaya ga hanyar Allah. Allah Ya taimake shi Ya qara masa shahara da iko, ya kuma qarfafa shi da taimakonsa ya kuwa yawaitar da mataima kansa. Ya roqe ni da in rubuta masa wasu kalmomi waxanda suka qunshi qa'idojin siyasa da kuma misalai da suka kamata a bi ga matsalolin da suka shafi shugabanci. Na karva masa roqonsa bayan da na yi istihara ga Allah. Wanda daga wajenSa ne kawai ake neman taimako."[2]

A farkon littafin Bello ya yi bayani game da daraja da kuma muhimmancin shugabanci da kuma haxarin da ke tattare a ciki ga wanda ya qi ya yi aikinsa yadda aka umurta. Ya kuma ambaci sakamakon wanda duk ya gudanar da mulkinsa akan qa'idojin da aka shimfixa a cikin Qura'ni da Hadisi. Daga cikinsu akwai maganar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da ya ce:

"Ko kuna son in yi muku bayani game da sarauta da kuma micece ita? Sahabansa suka ce masa i, ya Manzon Allah. Ya ce: farkon ta dai shi ne zargi,

---

[1] Shi wannan littafi ba'a rubuta tarihin wallafa shi ba, na ma'aikatar Tarihi ta Jihar Sakkwato da lamba haka AMSS1/4/82/280. Yana xauke ne a *Mujallar Hukumar Tarihi ta Jihar Sakkwato*.

[2] *Mujallar Hukumar Tarihi Ta Jihar Sakkwato Na Xaya*, shafi na 81.

tsakarta kuwa danasani, qarshenta kuwa azabar ranar qiyama. Haka kuwa ya faxa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa: 'Adalcin shugaba na rana xaya ya fi ibadar shekaru saba'in. A ranar Alqiyama babu wata inuwa babu kuwa wata mafaka da za a samu sai dai inuwar Allah. A wannan rana mutum bakwai za su zauna a qarqashin inuwarSa. Sarki mai adalci ga talakawansa, da saurayi wanda ya tashi a cikin bautar Ubangijinsa, da mutum wanda ko kasuwa amma zuciyarsa na masallaci, da kuma mutane biyu da suka so juna ta hanyar bautar Allah, da kuma mutum wanda ya zubar da hawayensa a lokacin da ya tuna da Allah a lokacin kaxaitarsa. Kuma da mutum wanda kammalallar mace mai-kyawo wadda kuwa yake so ta kira shi (ga zina) ya ce mata: Ina tsoron Allah Mai-girma da Xaukaka. Haka kuma da mutum wanda ya ba da sadaka a voye da hannunsa na dama amma bai bari hannunsa na hagu ya san abin da dama ta bayar ba.

"Bayan haka Bello ya furta cewa azaba na jiran duk wanda ya qi ya gudanar da abubuwan da suka wajaba ga shugaba. Haka kuma zai cimma azaba wadda ba ta misaltuwa. Ya kuma ruwaito waxansu Hadisai domin qarfafa wannan Magana ya ce:

"Dalili a kan nauyi da muhimmancin shugabanci shi ne: abin da aka ruwaito daga Abdullahi xan Abbas Allah Ya yarda da shi cewa 'wata rana Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya yi tsaye ga qofar Ka'ba, a lokacin nan kuwa Quraishawa da yawa na cikin qakin. Annabi ya ce: 'Ya ku shugabannin Quraishawa: ku yi mua'mala da talakawanku da abubuwa uku, idan suka roke ku da ku tausaya masu, to ku tausaya masu, idan kuwa kuka yi hukunci tsakaninsu to ku yi a'dalci, haka kuwa aikinku ya da ce da maganarku. Duk wanda kuwa yaqi ya aikata haka la'anar Allah da Mala'ikunsa ta tabbata a kansa, kuma Allah ba zai karvar ma wannan mutum ayyukansa ba na farilla ko kuwa na sunna.

"Ya kuma faxa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa: 'Duk wanda ya yi hukunci tsakanin mutum biyu masu husuma ya kuma yi zalunci, ku sani la'anar Allah ta tabbata ga waxanda suka yi zalunci. Haka kuma ya faxa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi '. Akwai waxansu mutane uku da Allah ba Zai yi duba a gare su ba a ranar Qiyama: maqaryacin shugaba, da tsoho mazinaci da kuma talaka Mai girman kai.

"Wata rana Annabi ya faxa wa Sahabansa cewa 'lokaci zai zo da za ku sami nasara ga mafi yawan qasashe na Gabas da na Yamma, za su kuma zama ga hannuwanku. Duk kuwa waxanda suka karvi muqamai, suna cikin wutar Jihannama sai fa waxanda suka tsoraci Allah Mai girma da Xaukaka, kuma suka bi hanyar taqawa suka kuwa gudanar da mulkinsu da gaskiya.

"Kasancewar duk wannan abu da ya gabata kamar gabatarwa ne ga littafin, bayan ambatar Hadisai da duk ababen da suka gabata, sai Bello ya shiga yin Magana akan qa'idojin siyasa. Mai yiyuwa ya yi wannan gabatarwa ce domin ya

jawo hankalin mai-tambaya ga cewa lallai abin da yake tambaya akai matsala ce Mai girma. Qa'idojin siyasa ko kuwa gimshiqan siyasa kamar yadda Muhammadu Bello ya ambata a nan guda bakwai ne, kuma dukkan bakwai xin suna nuna abu xaya wato dai adalci. Ya ce:

"Ku sani cewa qa'idojin siyasa bakwai ne waxanda dukansu ke nuna ma'ana xaya wato adalci. Adalci shi ne siyasa xunguminta. Biyu daga cikin waxannan qa'idoji sun shafi Sarki ko kuwa Gwamna ko Shugaba. Wasu biyu kuwa suna Magana ne a kan 'yan majalisar Sarki da kuma ma'aikata a halin da sauran uku ke magana game da talakawa:

1. Bayan haka sai ya shiga magana akan qa'ida ta farko wadda ta qunshi sharuxxan da sai an same su, sa'an nan mutum zai zama ya can canci shugabanci. Wannan ba tare da kulawa da laqabin da za a kira shi ba. Duk xaya ne ko a kira shi Sarki ko Shugaba ko Gwamna. A ganin Muhammadu Bello waxannan sharuxxa shida ne, su ne kamar haka:

"Shugaba ko Gwamna wajibi ne ya zama mai taqawa ga addininsa, kuma mai bin sunnar Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi. Wajibi ne ya zama mai kula da al'amuran lahira. Haka kuwa ya zama mai tsayuwa ga dokokin Allah, kuma kada ya zama mai son duniya. Haka kuma kada ya nuna kwaxayi ga shugabanci ballantana ya karkatar da hankalinsa ga son shugabancin.

"Bayan haka, sai ya yi magana a kan bayar da sarauta da cewa ba ya halatta a bayar da ita ga wanda ya neme ta. Duk da kasancewar babu wata takamaimar magana daga Annabi da ke umurni da a nemi shugabanci maimakon haka ma, Annabi ya yi hani da bixar ta, sai fa idan an nemi mutum ya yi. Duk da haka dai Bello ya faxi wannan magana da ke biye: "Ya zama wajibi a naxa shugaba da mataima kansa, kamar su Waziri, Sarki da Alqali ga kowane yanki na qasa. Domin kare addini da tabbatar da zaman lafiyana duniya."

2. Sa'annan ya ci gaba da bayani akan qa'ida ta biyu yana mai cewa:

Qa'ida ta biyu ita ce Shugaba ko kuwa Sarki ko Gwamna dole ne ya zama mai alheri, wanda yafewarsa ta fi fushinsa yawa. Wajibi ne kuma ya zama mai karimci mai kuwa jurewa. Tilas ne kuwa ya zama mai sadaukar da rayuwarsa. Saboda shugaba idan bai zama mai alheri ba, kuma wanda yafewarsa ta fi fushinsa yawa, kuma mai son karimci kuma mai halin jurewa, ana jin tsoron cewa mutane za su gaji da shi kuma su yi watsi da al'amarinsa kamar dai yadda Allah Mai girma da Xaukaka ya ambata "saboda wata rahama ce daga Allah ka yi sanyin hali a gare su. Kuma da ka kasance mai kaushi, mai kaurin zuciya, da sun watse daga

gefenka. Sai ka yafe masu laifinsu. (Sura Ta Uku, Aya Ta: 159)"[1] Idan bai zama zarumi ba ana tsoron ya rikice a lokacin da wata musiba ta sauka, ko kuwa ya ximauce a lokacin bala'o'i. A dalilin haka harkokinsa sai su yi rauni, al'amuran talakawa kuma su lala ce. Abu ne mai kyawo wajensa ya zama mai qarfin zuciya, wanda bai girgizuwa; wanda bai fita daga hankalinsa ba a lokacin da fushi ya same shi. Haka kuwa ya zama wanda ba zai sauya ba wajen taimako ga ma'aikatansa da talakawansa. Domin ya zama makoma ga talakawansa a lokacin da suke neman taimako ga wani abu da ya tsoratar da su ko kuwa ya rikita masu al'amura. Idan bai zama mai karimci ba, ana tsoron ya zama mai rowa wajen bayar da haqqin talakawa ga Baitulmali ta hanyar da ta kamata. Ana kuwa zaton mutane su yanke mu'amala da shi su kuwa riqa zarginsa, wanda yake al'amari ne da bai da ce ba.

3. Sa'annan Bello ya shiga yin magana game da qa'ida ta uku yana mai faxar cewa:

Shugaba ko Sarki ko kuwa Gwamna tilas ne a ko yaushe ya zama mai begen saduwa da malaman addini, ya kuma zama mai-tsananin so da saurare ga nasihohinsu. Haka kuma ya kiyayi miyagun malamai waxanda ke kwaxayin samun duniya, waxanda kuwa ko yaushe suke yabonsa su girmama shi, su kuwa bixi yardarsa ba don komai ba sai don abin da ke hannunsa na dauxar duniya da kuma haramiya. Ba don komai ba suke haka a'a sai don su sami wani abu daga gare shi ne wannan dauxar ta biyar muguwar hanya da kuma yaudara.

Malamin qwarai shi ne wanda bai sha'awar abin da ke hannunka na dukiya, kuma mai-mu'amala da kai da gaskiya tare da yi maka wa'azi da huxubobi. Bayan wannan sai Bello ya bayar da misalai uku na nasihohi da *Shaqiqul Balhi* ya fada wa halifa Haruna Rashid a lokacin da ya zo fadarsa. A nasiha ta farko Shaqiqul-Balhi ya gaya wa Haruna Rashid cewa Allah na neman shi da ya yi aiki irin na Abubakar, da Umar, da Usmanu da Aliyu Bello ya ce:

"Wata rana Shaqiqul-Balhi ya tafi fadar Haruna Rashidi, sai Haruna ya ce masa ko kai ne, Shaqiqu Taqiyi? Shi kuma ya ba shi amsa da cewa 'a'a ni dai ne Shaqiqu amma ba taqiyi ba'. Sa'annan Haruna ya ce masa: 'Ina son ka yi min nasiha', shi kuwa ya ce masa: 'Allah Mai girma da Xaukaka ya zaunar da kai ga Mahalli na Abubakar Sadiqu, saboda haka yana neman ka da ka yi gaskiya irin tasa. Ya kuma yi maka baiwa da mazaunin Umar xan Haxabi wanda ake kira Faruqu, yana kuwa buqatarka da ka rarrabe tsakanin gaskiya da qarya tamkar yadda ya yi. Ya kuwa ba ka matsayin zunnuraini Usmanu yana kuma bixar kunya

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi ta Jihar Sakkwato*. shafi na 87-88.

da karimci irin nasa daga wajenka. Haka kuma ya baka matsayin Aliyu xan Abu Talib yana kuwa buqatar ilimi da adalci irin nasa daga gare ka."

Sa'annan aka biyo wannan magana da nasiha ta biyu; Bello ya ce:

"Sai Haruna ya ce: "Ka qara mini wata nasihar", Shaqiqu ya ce: " na'am ka sani Allah Mai-Girma da Xaukaka na da wani gida da aka sani da sunan Jihannama, ya kuma sanya ka, ka zama mai-tsoron wannan gida. Haka kuma ya ba ka abubuwa uku su ne: Baitu-Mali, da bulala da kuma takobi. Ya umurce ka da ka hani mutane da shiga Jihannama da waxannan abubuwa uku. Idan mabuqaci ya zo ma da buqatarsa to kada ka hana masa dukiyar Baitu-Mali. Kuma duk wanda ya kaucewa umurnin Allah Mai-girma da Xaukaka, ka yi masa horo da wannan bulalar. Haka kuma duk wanda ya kashe wani, ba da haqqi ba, shi ma sai a kashe shi da wannan takobi tare da izinin Waliyyin wanda ka kashe. Idan kuwa ba ka aikata yadda ya umurce ka ba, to lallai za ka zama jagora da shugaban waxanda aka hukunta shigar su wuta.

Sa'annan aka biyo da bayani game da nasiha ta uku:

Haruna ya ce "ka qara mini wata nasihar." Shaqiqu ya ce: "Mutum irinka kamar marmaro ne, sauran mutane kuwa na duniya tamkar na'ura ce ta shayar da ruwa. Saboda haka, idan marmaro ya kasance mai-tsabta, qazantar na'ura ba za ta cutar da shi ba. Ta wani gefen kuwa, idan marmaro ya zama mai qazanta to zaman na'ura da tsabta ba zai amfanar ba."

Anan nasihar da Shaqiqu ya yi wa Halifa Haruna Rashidi ta qare. Bayan haka sai Muhammadu Bello ya ci gaba da magana game da fadawan Sarki. Ya ce:

Idan ya zama bai hulxa da malamai managarta da kuma sauraren nasihohinsu idan ya zama mai hulda da miyagun malamai da xaukarsu tamkar abokai, to lallai za su tilasta masa, da ya bi hanyarsu, ko kuwa mutane su yi zaton haka. Saboda mutum ana zaton ya kwaikwayi abin da na tare da shi ke yi. Masu hikima sun faxi cewa: kada ka tambayi halin mutum a'a tambayi abokansa, haqiqa aboki mai kwaikwyo ne ga abin da abokinsa ke aikatawa.[1]

4. A game da qa'ida ta huxu, ita wannan qa'ida ta qunshi sharuxxan da ke cancantar da mutum da ya riqi wani muqami. Haka kuma ta qunshi waxansu nassosi waxanda suka yi bayanin siffofi da xabi'un Halifa Umar a wajen kulawa da talakawansa. Bello ya ruwaito waxannan misalai domin ya nuna yadda ya kamata shugaba ya yi mua'mala da talakawansa. Ya ce:

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi ta Jihar Sakkwato*. shafi na 89-92.

"Qa'ida ta huxu ita ce, Shugaba ko Sarki ko Gwamna wajibi ne a gare shi ya sanya a'dalci ya zama sharaxi ga duk wani da ke son ya riqi wani muqami. Haka kuma tilas ne ya zavi ma'aikatansa daga cikin mutane na kirki. Haka kuma ya wajaba a gare shi da ya riqa duba ayyukansu ga dukkan lokatai.

"Asimu xan Bahzata ya karvo cewa: a ko yaushe Umar xan Haxabi ya nufi ya naxa Gwamna ya kan sa masa sharuxxan cewa kada ya hau zavavven doki, dole ne ya sanya tufafi irin waxanda talakawansa ke sanyawa, haka kuwa yaci nau'in abinci da suke ci, haka kuwa kada ya rufe qofarsa ga masu neman taimakonsa domin su sami abin da za su kyautata halolinsu. Ya kan gaya wa ma'aikatansa cewa: 'ba'ina naxa ku ba ne domin ku ci mutuncinsu ko kuwa domin kawar da manufofinsu ba, a'a ina naxa ku ne domin ku yi masu limanci wajen salla, ku kuwa yi hukunci a tsakaninsu, sa'an nan kuwa ku raba komai kuka ci ko kuka sha a gare su.

"Umar xan Haxabi wata rana ya rubuta wa shugaban ma'aikatansa Abu Musa Al-Ash'ari cewa: fiyayyen shugaba shi ne wanda talakawansa suka wadata a qarqashin mulkinsa. Shugaba kuwa marar sa'a shi ne wanda talakawansa ke baqin ciki da shi. Ya ce masa kuwa yi hankali kada ka yi zalunci, domin idan ka yi haka ma'aikatanka za'su yi koyi da kai. Mutum irinka kamar dabbobi ne da suka sami makiyayi mai tatse su idan suka yi kiyo sosai, suka kuma yi qiba. Wannan qibar ita za ta zama dalilin halakarsu, saboda za a yanka su a kuma ci a dalilin wannan qiba tasu."

A lokacin da yake bayani a kan wannan qa'ida, Muhammadu Bello ya tavo maganar ma'aikatan Sarki da masu yi wa Sarki hidima da sauran jama'ar da ke fada, yana mai cewa shugaba wajibi ne ya kula da ma'aikata da masu yi masa hidima musamman ma iyalan gida. Saboda su kan so ga shugaba ya yi zalunci maimakon adalci domin ta haka ne kawai za'su iya cimma manufofinsu da abubuwan da suke sha'awa. Muhimmin abu ne ga shugaba ya san cewa waxannan mutane suna aiki ne domin halakarsa, haka kuma suna yin hidimarsu ne saboda kuxi. Ga yadda yake faxa:

> *Abin da a magani shi ne ya kula da ma'aikata da masu hidima waxanda yake saboda manufofinsu su kan yaudari Gwamna su kuwa nuna masa da ya yi zalunci, a dalilin haka sai su jefa shi a cikin wutar Jihannama, ba don komai ba, a'a sai don cimma burinsu.*
>
> *Shin ko akwai wani maqiyi mai-tsananin qiyayya kamar maqiyin da ke famar zuwa ga halakar da kai? A cikin littafin da ake kira Al-itibar an faxa cewa: ma'aikata da masu hidima mafi-yawansu masu bauta wa cikkunansu ne, da mata da kuma sha'awa. Su kan mayar da Sarkinsu kamar koma domin su cimma sha'awar su. Haqiqa dukkan*

ayyukansu suna yi ne domin kansu amma ba donsa ba. Alamun haka shi ne da'a ce sun sami labarin cewa za a karve sarauta daga gare shi, da ka gansu, sun juya gaba xaya zuwa ga wancan wanda za a bai wa sarautar. Saboda a kowane wuri ya zama akwai kuxi, to za'su yi bauta a wannan wurin su kuwa yi sujuda a gare shi.[1]

5. A game da qa'ida ta biyar Bello ya ce:

Qa'ida ta biyar ita ce: Shugaba ko Sarki ko Gwamna ya zama yana umurtar talakawansa da su yi adalci su kuma zama masu karimci da kuma su nisanta daga aikata miyagun ayyuka. Wajibi ne kuma ya yi masu jagoranci ga salla ya kuma umurce su da su aikata abubuwa masu kyawo su kuwa qi marasa kyau.

Duka-duka dai halayen shugaba suna da dangane da halayen talakawansa da kuma ayyukansu. Saboda haka idan talakawa suka yi aiki mai-kyau wajen Ubangijinsu Allah Mai-Girma da Xaukaka to Allah zai sanya jin-qayi ga zukatan shugabanni, su aikata abubuwa na kirki ga talakawan. Amma idan talakawa suka qi biyar umurnin Allah suka zama mavarnata a cikin qasa to Allah zai ba shugabanni iko a kansu, su riqa munana masu. Allah Mai-girma da Xaukaka ya ce: "Kuma kamar wancan ne muke jivintar da sashen azzalumai akan sashe" (Sura Ta Shida: Aya Ta: 129). A cikin Hadisi kuma an ruwaito cewa: "Za a shugabance ku tamkar yadda kuke."

6. Bayan haka sai qa'ida ta shida, wannan qa'ida na magana ne a kan kula da gyaran daular musulunci. A cikin wannan qa'idar Bello ya ambaci waxansu shirye-shirye waxanda idan abin a zartar da su ne, to lallai daular Musulmi za ta zama mai-qarfi kuma mai-dogaro da kanta; ya ce:

Qa'ida ta shida ita ce: wajibi ne ga Shugaba ko kuwa Sarki ko Gwamna ya yi qoqarin tanadi da aiwatar da ayyukan duniya da na lahira ga jama'arsa. Haka kuma ya zama tilas gare shi da ya yi aiki tuquru ya kuwa mayar da himmarsa ga sana'o'in hannu ya kuma qarfafa guiwar masu sana'o'i: kamar su manoma da maqera da maxunka da kuma marina.

Waxansu kuwa su ne likitoci, masu sayar da kayan gona, mafauta da kafintoci da dai kowane irin sana'a wadda za ta taimaka ga kawo

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi ta Jihar Sakkwato*. shafi na 92-95.

zaman lafiya a duniya. Wajibi ne shugaba ya qarfafa su ga qasa a cikin kowane gari da kuma kowane qauye. Haka kuma ya umurce su da su yi tsimin abinci. Wajibi ne kuwa a kansa kuma ya umurce su da raya alqaryu, qauyuka da kuma gina tasmaharori da gadoji. Ya kuwa hore su da su kula da kasuwanni da gyaran hanyoyi. Ya zama wajibi kuwa a gare shi ya samar da dukkan ababen jin-daxi ga jama'arsa domin a sami cikakken zaman lafiya a wannan duniya.

Aliyu xan Abu Xalib ya faxa a cikin littafin da ake kira Jauhara cewa: wata rana ya ga Umaru xan Haxabi yana sammakon tafiya zuwa wani wuri, ya ce: sai na tambaye shi ko a ina za shi, sai ya ba ni amsar cewa 'ina duban raqumi ne da aka bayar zakka'. Sai na ce 'Ya ka wulaqantar da shugabannin da za su zo bayanka'. Ya ce 'kada ka zarge ni ya kai baban Alhasan, na rantse da wanda ya aiko Muhammad da Annabci, da a ce xan-rago ya halaka ga gavar qoramar Furatu, Umar ne za a tambaya game da shi a ranar qiyama. Saboda babu wani girma ga kowane shugaba da ya yi sakaci ga al'amuran Musulmi. An faxa a cikin littafin da ake kira Shibrahiti cewa wani daga cikin annabawan bani-Isra'ila ya tambayi Allah dalilin tsawon rayuwar Sarakunan Farisa, Allah Ya bayyana masa cewa dalilin haka shi ne sun ni'imtar da qasa ga bayina domin su zauna a ciki. Haka kuma abu ne da ya zama wajibi ga shugaba ya samar da ababen gudanar da Addini ga jama'a tasa ta hanyar gina masallatai domin jama'a su sami wuraren yin salla da kuma waxansu ayyuka na ibada. Ya kuma zama wajibi a kansa da ya naxa alqalai da malamai (masu bayar da shawara) ya kuma biya su haqqinsu daga dukiyar Baitu-Mali. Haka kuma ya sanar da malamai masu koyar da yara da masu huxuba (a masallatai) da muhtasibobi (wato waxanda za su kula da gyaran kasuwanni da kuma kula da halayen jama'a dangane da biyar shari'a). ya kuma wajaba a kansa ya sami masu tara zakka da masu leqen asiri domin su nemo masa labarin waxanda aka zalunta da kuma marasa galihu.

A cikin littafin da ake kira Jauhara Hasanul-Basri ya ruwaito cewa wata rana Umar xan Haxabi na yawo da dare a garin Madina, sai ya haxu da wata mata xauke da salka ta ruwa, sai Umar ya tambaye ta ko mene ne xauke da shi. Ita kuwa ta ba shi amsa da cewa tana da yara, amma ba ta da mai yi mata hidima. A dalilin haka take fita ko yaushe da dare domin ta samo masu ruwa. Haka kuma ta gaya masa cewa ba ta son ta fita da rana. Sai Umar ya xaukar mata salkar ya kai mata har gidanta. Sa'annan ya ce mata 'gobe da safe ki tafi wurin Umar zai yi miki hidima'. Sai ta gaya masa cewa za ta yi haka.

Hasanul-Basari ya ce, sai ta tafi can, a lokacin da ta isa, sai ta gane cewa ashe Umar ne ya xaukar mata salkar ruwanta, saboda haka sai ta juya. Sai Umar ya aika aka kira ta, ya kuwa yi umurni da a ba ta mai-yi-mata hidima da kuma kuxin abinci.[1]

7. Wannan ita ce qa'ida ta bakwai wadda a cikinta Bello ya faxi yadda ya kamata shugaba ya yi mua'mala da talakawansa. Haka kuma a cikin wannan qa'ida ya yi magana game da rabe-raben shari'a guda uku, wato Qur'ani da Hadisi da kuma Haxuwar malamai. Ya faxa cewa duk wata doka da Allah Ya wajabtar a cikin Qur'ani ko kuwa Annabinsa ya wajabtar da ita a cikin Hadisansa ko kuwa ta zama doka ce da malamai suka haxu a kan wajabcinta, to ta zama tsayayyar doka wadda ta wajaba ga Musulmi ya bi. Idan aka qi biyar irin wannan doka, to, shugaban qasa ta musulunci na da damar ya tilasta jama'a da su bi wannan dokar ta hanyar amfani da kowa ce irin hanya ta sauqaqa.

Amma game da dokoki waxanda suke ajizai, shugaba na musulunci ba ya da halin tilasta jama'a da su bi waxannan dokoki koda kuwa jama'a sun qi su bi waxannan dokokin. Bello ya ce:

Qa'ida ta bakwai ita ce Sarki ko shugaba ko Gwamna dole ne ya yi mua'mala da talakawansa da alheri. Abin da ake nufi da wannan shi ne, dole ya sanya shugabanni daga cikinsu su yi aiki dai-dai da abin da ya fi dacewa, kowane xaya daga cikinsu gwargwadon matsayinsa.

A game da talakawa kuwa, ba ya halatta ya xora masu ababe waxanda ba su wajaba a kansu ba, ta wajen harkokin addini da kuma na duniyarsu. Dole ne kuma ya yi qoqari ya karantar da su Tauhidi domin su san Ubangijinsu. Ya kuma umurce su da su aikata abubuwa waxanda suka wajaba a kansu, ya kuwa hana su aikata ababen da aka haramta. Kada kuwa ya zama mai-matsatsi game da ababen da aka yarda da a aikata (wato mubahi) koda kuwa su waxannan ababen savanin malamai ya auku a kansu. Haka kuwa kada ya tsananta masu game da ababe waxanda malamai suka yi savani akan wajibansu ko haramcinsu, ballantana daxa ababen da ake zargi. Gaba xaya dai bai kamata a gare shi ba ya yi gaugawa ga vata ayyukansu ko kuwa aqidarsu.

Haka kuwa ba ya halatta ya vata ibadarsu ko kuma mua'malolin cinikayyarsu, idan dai ya zama yana dogara ne ga waxansu ra'ayoyi

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi ta Jihar Sakkwato*. shafi na 96-99.

da wani mijtahidi ya shimfixa ta hanyar fahimtarsa, amma ba tare da an ambaci wannan matsalar ba sosai-da-sosai a cikin Kur'ani da Hadisi. Sai fa lokacin da suka aikata wata matsala wadda ta karya ijma'i na malamai, to a wannan lokaci sai ya nemi su bi wannan ijma'i domin doka ce da Allah Ya yi izini da abi. Amma game da abubuwan da aka ciranto na dokoki waxanda ba na Allah ba Mai-girma da Xaukaka, to waxannan dokoki ne kawai na bayinsa waxanda malamai suka yi savani a kai. Don haka Allah ba Zai tambayi bayinSa ba game da su a ranar qiyama.

Bayan haka sai Bello ya kawo Hadisi wanda ya qunshi zargin da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi wa Mu'azu a lokacin da ya tsawatar da karatun Qura'ni ga salla. Ya ce: "Annabi ya ce daga cikinku akwai masu firgitar da waxansu."

Bello ya zo da wannan Hadisi ne domin ya tabbatar da maganarsa da ta gabata cewa shugaba ba zai vata ayyukan jama'arsa ba, ko kuwa ya tsananta masu game da matsaloli da babu ijma'i na malamai a kai, ko kuwa waxanda ba su da asali a cikin Qura'ni ko Hadisi. Kafin ya qare littafinsa Bello ya yi magana game da xabi'u da halayen Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, wajen mua'mala da talakawansa, ya ce:

"Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, shi ne mafifici wanda ya fi kowa ga ilimi da kuma tsoron Allah. Ya kasance yana mua'mala da jama'a gwargwadon halayensu. Ya jure wa matsananciyar mua'malar da Larabawa suka yi masa da kuma cutarwar munafikai har aka ce masa "ka tsaurara a kansu" (Sura ta tara: Aya ta: 73). Ya kuma kasance yana hulxa da shugabanninsu da kuma ba su dukiya mai yawa domin jawo hankalin waxansu zuwa ga Imani ko kuwa domin tabbatar da Imani a cikin zuciyoyin waxansu domin su tabbata a cikinsa."

A qarshen littafin ya ce:

Kowane mutum ya karanci littaffan tarihi game da halayen Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, zai ga waxansu ababe da aka ambata game da halayen Annabi. Allah Mai-girma da Xaukaka ya ce: "Lallai ne haqiqa Manzo daga cikinku ya je muku. Abin da kuka wahala da shi mai nauyi ne a kansa. Mai kwaxayi ne saboda ku. Ga muminai mai tausayi ne mai-jinqayi."

To, idan sun juya sai ka ce: Ma'ishina Allah ne. Babu abin bautawa fa ce shi. A gare shi nake dogara kuma shi ne Ubangijin Al'arshi Mai-girma. (Sura ta goma: aya ta: 128-9)."[1]

Littafin *Usulus Siyasati* ya taimaka, zai kuma taimaka wajen kafa tabbatacciyar siyasa a wannan zamani, saboda wannan littafi na koyar da komai da komai da ya shafi matsalar shugabanci. Idan shugabanni suka zartar da abubuwan da littafin ya kawo, babu shakka, tabbatacciyar siyasa za ta kafu, a dalilin haka kuma wahalhalun da talakawa ke fama za su gushe, ko su yi qaranci sosai. A kan wannan siyasa ce, Sarakuna ke mulki kafin tavarvArewar mulkinsu, wanda Turawa suka ture a shekarar 1903. Amma duk da haka qaidojin da Sarki Bello ya kawo, akan siyasa su na nan, amma bin da aka rasa yi, shi ne zartar da waxannan shika-shikan shugabanci, don haka aka samu tavarvArewa sha'anin shugabanci a wannan zamani a yau. Adalci a shugabanci ya yi qaranci duk da cewa musulunci ya bada alhairai masu yawa ga yin adalci: "adalcin rana guda ya fi Ibadar shekarar saba'in!."

Tun a wancan zamanin Siyasar Farko an fahimci Arewa na fanxArewa daga kan waxannan shika-shikai na siyasa masu muhimmanci da suka samo tushe daga Daular Usumaniyya. Don an sami tangarxa a tsakanin 'yan Siyasa da Sarakuna abin da ya kawo givi babba wajen xorewar siyasa – tabbataciya. A dalilin haka ne ma M. Sa'adu Zungur a waqarsa: *Arewa, Jamburiya Ko Mulukiya*? Ya ce:

Babbar matsalar da ke addabar Arewa tun daga wancan zamani har ya zuwa yanzu, shi ne qin yin abin da ya kamata, ba rashin sanin abin da ya kamata a yi ba. Saboda haka babu jahilci a lamarin su. Ayyukan Baraden Daular Usumaniyya da rubuce-rubucensu babu shakka sun isa su kai mu ga ci gaban da zai zama abin misali a Afirka. A dalilin haka ne M. Sa'adu Zungur ya yi mana tanbihi a waqoqinsa, Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya. Don sun bar mana "dabarar sarrafa duniya." Amma saboda son rai wanda ya haifar da rashin kishi, sai "muka lalata muka wargaza" a dalilin haka a yanzu sai muka wayi gari "Ga shi yau sai anai mana dariya" Sa'annan kuma masifu sun kewaye mu ta ko ina! A kullum mu ne masu faxa da shugabanni da nuna matsanancin hamayya da qiyayya wajen neman shugabanci ido rufe. Ga shi ba dariya ake mana ba, a'a neman halaka mu ake yi ta kowane hali.

A kan qa'idojin da Alqur'ani Mai Tsarki da Sunna ta Manzon Allah (SAW), aka shimfixa tafarkin mulkin Sarakuna a Arewa. Wannan tafarki ne, masarauta ke kArewa, tunda daga zamanin Mujaddadi har gobe. Idan wani Sarki ya yi zalunci a sha'anin mulkinsa, shi shar'ia za ta hukumta, saboda ya kaucewa tafarkin

[1] *Mujallar Hukumar Tarihi Ta Jihar Sakkwato*, shafi na . 99-102.

masarautarsa. Abin da ya kamata shi ne a hukumta mai laifi kowanene shi. Amma hakan bai samu yiwuwa a zamanin Turawa ba don *Indirect Rule* ya karkatar da tsarin. A dalilin haka ne 'yan adawa da masarauta, sai su yi amfani da laifin wani Sarki don su vata sarauta baki xaya, alal misali, idan an sami Sarki da laifin aikata almubazziranci. Ya kamata mu san koyarwa Bello da kawunsa Shehu Abdullahi Wazirin Gwandu musamman akan shugabanci. Littafin Usulussiyasati wani hujja ne babba, da ke nuna yadda Sarakuna suka goge akan siyasa, da yadda su ke gwagwarmayar kawad da Lalaci da Zalunci da Jahilci, waxanda har yanzu sun yi wa Arewa katutu. Da Sarakuna na mulki da su ne za a xora wa laifin rashawa da tavarvArewar halayen jama'a.

Dimokuraxiyya mulki ne na Jama'a, amma wanda su jama'an suka zava saboda dacewarsu da kuma amincin da waxannan mutane suka baiwa waxannan shugabanni. Wannan tsari a na gani zai rage zalunci zai kuma kawo ci gaban jama'a. Da yake siyasa ita ce hanyar da ake bi wajen aiwatar da mulkin Dimukuraxiyya, wannan ya tilasta jama'a shiga siyasa domin su kawo masu abubuwan ci gaban jama'a tare da ababen more rayuwa. Amma wa su na da ra'ayin cewa, Siyasa ba sana'a bace, garkuwa cewadda za a yi amfani da ita wajen kare 'yanci da sana'a da kawo sauran abubuwan ci gaban xan-Adam. Kafin mutum ya shiga siyasa, wajibi ne ya riqe wata sana'arsa muhimmiya wanda aka san shi da ita. Domin idan mutane suka kira shi ya wakilce su ko kuma ya riqe wani muqami, duk waxannan akan yi su ne na wani tsawon lokaci kaxan. Idan mutum ya gama mulkinsa, sai, angulu ta koma gidanta na tsamiya, idan ba a sake zavensa ba.

Amma idan mutum ya xauka siyasa sana'a ce, to, babu shakka yana tare da nadama, ko ba baxe ko ba jima. Siyasa ba ta da xa, kamar duniya take, tana da ido ne a tsakar ka. Maganin siyasa riqe qwaqqwarar sana'a da tafiyar da mulkin adalci saboda sana'a ce za ta kare mutum daga zaluncin jama'arsa, a lokacin da yake kan mulki. Ita ce kuma za ta kare mutuncinsa lokacin da ya bar mulki. Dimukuraxiyya mulki ne na wakilancin jama'a. Saboda haka yana da lokaci qayyadadde.

Yana xaya daga cikin manufofin siyasa a haxa duka dangogin jama'a takan wakilansu a Majalisa, a matsayi daban-daban, inda za su iya sakewa su yi shawara kan buqatunsu da matsalolinsu, yadda ta haka za su tabbatar da cewa ana biyan buqatunsu na gaskiya. Haqqin waxannan wakilai ko shugabanni ne yin aiki gwargwadon buqata, kuma bisa yadda ya dace da kiyayewar iko da kuma gwargwadon hali.

Daga qasa kuma ga Sarakuna waxanda suke da jama'a tun fil azal, waxanda kuma suka tare su da su har yanzu har kuma gobe. A sama kuma ga zavavbun wakilai. Turawa sun lura da dangartakar da ke akwai tsakaninsu (Sarakuna) da jama'a. Sun kuma yaba da mulkinsu qwarai da gaske don haka ne Gwamna Lugga ya kawo mulkin *Indirect Rule*. Saboda ganin takarawar da suka yi, a lokacin

Mulkin Mallaka, ya tilasta a yi da su a lokacin siyasa, idan ana son mulkin Dimukuraxiyya tabbataciya. Siyasa mai kyau ta na tafiya ne da mutane masu jama'a, waxanda jama'a kuma suka amincewa. Wannan ya tilasta tafiya da Sarakuna a lokacin Siyasar Farko. Dalili kuwa mulkin dimokaraxiyyana canzawa, a wurare daban-daban saboda bambancin al'adu da addini, amma kuma manufarta guda xaya ce: tabbatar da adalci da 'yanci ga kowa.

Dimukuradiyyar a qasashen Afirka ta bambanta da ta Turai. A kuma qasashen akwai 'yan bambance bambance a tsakanin qasashe da qasashe. Akwai qasashen da Sarakuna ko shugabanni suka rasa tasiri a zuwan Turawa, amma akwai wasu qasashen da tasirinsu ya daxa qaruwa, kamar Sarakuna da shugabannin Nijeriya ta Arewa. Su ne suke faxa a ji, suke kuma tare da jama'a qut-da-qut a kowane lokaci. Idan aka raba Sarakuna da siyasa, kamar an raba hanta ne da jini. Saboda haka raba Sarakuna siyasa, ya illata, ya kuma raunata qarfi da darajar siyasa a Nijeriya. A siyasar farko Sarakuna sun taka rawar gani a wannan Zamani. Don haka ne 'yan Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna ke tafiya kafaxa da kafaxa, kamar fuka-fukan jirgin sama, wajen dai-daituwa da cimma manufa, kafin mulki ta kan Sarakuna ya zo qarshe. Da farko *Indirect Rule* bai ba Sarakuna shiga siyasa ka'in da na'in ba, sai daga baya. Sarkin Musulmi a bisa tsarin Daular Usumaniyya shi ne shugaban Majalisar Sarakuna.

Majalisar Sarakuna

Manya-manyan Turawan Mulki sun yiwa Sarakuna babbar fahimta sosai. Da yawa sun yaba masu wajen gogewa da mulki da kuma jurewa wahalhalu da nauyin jama'arsu. A lokuta daban-daban Sir Bryan Sharwood Smith ya kan furta yabonsa ga Sarakunan Arewa. Waxanda ya yi masu kyakkaywan nazari kuma yake basu kyakkyawar shawara shi ne Sir Palmer, wanda ya daxe a wannan qasa yana tu'ammuli da jama'arta. Shi ne ma ya qara tsunduma Sarakuna cikin siyasa ka'in da na'in don a sami ci gaba. A dalilin haka ne aka samu kafuwar Majalisar Sarakuna.

Sir Richmond Palmer K.C.M.G, C.B.E., Leftanan Gwamna na Lardunan Arewa, shi ya ba da shawara da Sarakunan Arewa su riqa yin taro a wuri xaya don su riqa ba da shawarwari abubuwan da za su amfani qasashensu baki xaya. Sun kuma karvi wannan shawarwari Gwamna. Wannan taro shi ne ya zama Majalisar Sarakuna a Arewa da Yamma, kuma ya qara aminci tsakanin Sarakuna.[1] Wato shi ya sa qara nutsa Sarakuna a siyasa a zamanin mulkin Ingilishi. Da yake Kaduna ce cibiyar wannan taro, sai garin ya qaru, da gine gine da bunqasa da manyan mutane. Wannan taro kuma sai ya zama salsalar ba da gudunmawar Sarakuna a

[1] C.R Niven, *Labarin Nijeriya*, shafi 107

mulkin siyasa ta fannoni daban-daban. Ko da yake dama a na bin mulkin Arewa takan Sarakuna da shugabaninsu kafin a kafa mulkin Dimukuraxiyya.

A dalilin haka aka kafa taron Sarakuna na shekara shekarar a 1931 wanda ya zama Majalisar Sarakunan Jihan Arewa.[1] Ita wannan Majalisa mai muhimmanci, ta yi zamanta na biyu, a ran 11 ga watan Nuwamba 1931, a qarqashin shugabancin gwamnan Kaduna, Sir Donald Cameron, K.C.M.G., K.B.E da kuma mataimakinsa Mista C. Alexandar C.M.G. A wannan taro na su, mai laqabi, *The Advisory Council*, wato Majalisar ba da Shawara, an tattauna batutuwa masu amfani da suka shafi Arewa da jama'arta. Abubuwan da aka nemi a tabbatar da su, a cikin wannan shawarwari da suka yi, sun haxa.

Da farko dai akwai maganar kafa Makarantar Sharia, wato *Law School*, ga maganar yangadi da 'yan Doka da Baitu-Mali. An kuma tattauna yiwuwar baiwa"yan doka bindiga in da hali. An kuma yi bayani akan amfani da zanen 'yanyatsu don tabbatar da gaskiyar zargin aikata laifi, abin da ake kira *Fingerprint*. Haka kuma gwamnan ya tattauna da Sarakuna a kan batun kafa maxaba a don buga jaridu ko littattafai. Akwai maganar harhaqa rijiyoyi a wuraren da ake fama da wahalar ruwa. An kuma tattauna sosai akan maganar kiwon lafiya, da gandun daji, da Qudan tsando mai sa ciwon barci. An tattauna a kan waxannan abubuwa kafin a yadda da kafa su, sannan nan kowanne xan majalisar ya rattaba hannunsa wanda ke nuna amincewarsa."[2]a lllokacin da Turawa suka qwace mulkin Sarakuna suka kuma riqa mulkin qasa ta *Indirect Rule* sai suka ga wajibcin shigar Sarakuna Siyasa amma a matsayin masu bada shawara wannan illar mulkin mallaka cewadda ta maida mulki mai bada sha'awa.

Tun a shekarar 1931, Majalisar Sarakuna ke taka rawar gani wajen bayar da shawara da himmatuwa wajen ganin an yiwa jama'arsu ayyukan ci gaba da jin daxin jama'a.Wato suna yin ayyukan da 'yan siyasa ke yi. A inda aka bambanta shi ne wajen hawa karagar mulki kawai 'yan Majalisar zaven su aka yi. A gaban gwamnan Kaduna, a kuma qarqashin wannan Majalisa ne, Sarakuna ke cashewa da sussuke wa su kuma sheqe wahalhalun da ke addabar jama'arsu da garuruwansu. Su kuma tsaya tsayin daka su ga an aiwatar da ayyuka muhimmai a garuruwansu. Wannan abu ya qara bunqasa ayyukan masarautunsu da, mulkin En'e wanda kuma ya qara qarfi da faxi a Arewa. A wannan zamani babu Majalisar Wakilai ci gaban Arewa kuma bai sami illa ba ko kaxan. A lokacin ma ba a fara Siyasa a Nijeriya ba. Irin wannan salon mulki ya baiwa kowa sha'awa, har ma Sardauna ya ce: "Ina kuma tsammani xaya daga cikin sha'anoni masu amfani na mulkin nan na En'e, idan an sa hangen nesa, shi ne wani abu wanda shekara ashirin da suka wuce, babu mai yin tunani kansa. Wato wannan abu kuwa, shi ne

---

[1] John Paden, *Religion and Political Culture in Kano*, shafi na 306

[2] Alqali Husaini Sufi, *Musan Kammu*, shafi na 252.

yadda ma'aikatan En'e suka yiwo gaba wajen tafiyar da al'amuran jama'a. Ko da yake yanzu an fara samun waxansu waxanda ba ma'aikatan En'e ne ba, amma duk muqamin Ministoci (har da ma'aikata) na Jihar duk ma'aikatan En'e na da suke riqe da su. Tun ma ba a je da nisa ba, ni kaina nan ma'aikacin En'e ne, har kwanan gobe kuwa idan aka tashi tsara istimat na Sakkwato za a sa ni ciki, ko da yake dai ba za a ambaci waxansu kuxi da za a biya ni ba."[1]

Ita wannan Majalisa ta yi tasiri akan mulkin En'e, shekaru masu yawa kafin zuwan sabon Tsarin Mulki. Saboda haka za a ga cewa harsashin ci gaban Arewa baki xaya Sarakuna ne suka kafa shi, sannan suka ci gaba da xora tubalan gininsa har ya kusan kai tsaiko, kafin vullowar 'yan makaranta.

Sir Bernard Bourdillon, gwamnan Nijeriya shi ya kawo wani ra'ayi na gyaran mulkin Nijeriya, wanda magajinsa Sir Arthur Richards wanda da ya zama Lord Milverton ya sami damar aiwatarwa. A cikin shekarar 1946 ne aka ci gaba da shawarwari a kan yadda za a kafa wa Nijeriya sabon Tsarin Mulki. Tsarin Mulkin da ake aiki da shi a lokacin, an tsara shi ne a shekarar 1922. wannan tsarin kuma bai tava dacewa tun daga lokacin da aka fara aiki da shi, jama'a ma ba su damu da shi ba sai daf da za a fara yaqi.[2] A shekarar 1947 aka a fara aiki da Tsarin Mulkin Richards, a lokacin ne aka yarda, 'yan Arewa su wakilci Arewa a Majalisar Dokokin Nijeriya. A zamanin MacPherson ne mulkin qasar ya kankama sosai. Sarkin Musulmi Sir Abubakar III ya yi maraba lale da zuwan wannan gwanin mulki.

Dabar Sir Macpherson

Farkon matakin da tsarin mulki *Richard Constitution* ya xauka shi ne kawo wa 'yan Nijeriya yin siyasa, wanda ya fara aiki daga shekarar 1943 zuwa 1949. A cikin watan Nuwamba a shekarar 1949, gwamnan Nijeriya, Sir Arthur Richards ya gama aikinsa a Nijeriya. Amma kafin ya yi ritaya, Mai girma Sarkin Ingila ya ba Gwamna Richards muqamin "Lord." A rana 11 ga Oktoban shekarar 1947, Mai girma Sarkin Ingila ya yarda da a riqa kiransa *Lord Milverton of Lagos and Clifton*.[3]

Da tashin Sir Arthur Richards, sai aka baiwa Sir John Macpherson ragamar mulkin Nijeriya. Shi kuma yana hawa gado, bai yi wata wata ba, sai ya ce zai fito rangadin Nigeriya ta Arewa. Wadda ita ce tagomashin jiha a Nijeriya. Sai ya qudiri niyyar da ya faro daga Sakkwato inda Mai Wandon Qarfe ke ranzdanci.

---

1 Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na . 106-107.

2 *Ibid.* shafi na 63.

3 GTK, 15/10/1946

Sakkwato ce cibiyar Daular Usumaniyya wato hedkwatar Arewa baki xaya kafin zuwan Turawa.

Da jin wannan shiri na Sabon gwamnan Nijeriya, sai Abubakar na uku, ba tare da vata lokaci ba ya shirya wata qwarya-qwaryar hawan ban girma don Sakkwato ta karrama wannan babban baqo. Aka kuma yi qasaitaccen Daba don ziyarar gwamnan Nijeriya. Sir Bryan, Razdan na Sakkwato a wannan lokaci, ya ba da taqaitaccen labarin wannan Daba mai ban sha'awa, inda ya ce:

> *Ran da zai iso na ga abu! Yadda Sarakunan Sakkwato suka shirya masa tarba, ai sai kallo! Duk karkara ta cika da doki. Sai gumzar ingarmu kake ji, da haniniyarsu, - Amirul Muminina, Abubakar ya tinqaro! Maso zama da kai ya yi Salla!*
>
> *Ban iya qidayawa ba, amma a qalla, doki alfen, dubu biyu sun dafo shi. Kowane mahayi yaci ado irin na azo a yi kallo. Amma shi ga ya can sanye da riga fara, qila ma ta alawayyo ce, irin ta malamai. Da ma al'adar ke nan. Amirul Muminina ba ya ado. A bisa kansa ga laima sai kaxa ta a ke yi. Duk karkara ta ruxe! bayin Sarki sai tavin dawaki su ke ta yi ana kai masa jinjina. Dogarawa suna karvawa – A gaisheku! Da ma tun kafin ya iso, Magajin Farai ya ba da labari a cikin farai cewa ga "Amirul Muminina nan ya tinqaro." Maroqa na kirari "Maso zama da kai ya yi Salla, jikan Mujaddadi!"*
>
> *Bayan wucewar, sai Sarkin Gwandu, sai na Argungu, sai na Yawuri. A bayansu su ma a qalla a sami jimillar doki dubu. Na tuna a wannan lokaci ne gwamnan ya waiwayo ni, cike da farin ciki, ya ce "Wata rana, ba da daxewa ba ina fata Mai martaba da Xaukaka, Sarkin Ingila, shi ma zai ga wannan al'amari da idonsa.*
>
> *Ka ji magana kamar ta malamin duba. Domin shekara takwas ba su cika ba, sai ga Sarauniyar Ingila a Kaduna.*[1]

Wannan Daba da aka yiwa Sabon gwamnan Nijeriya maraba da zuwa da ita tana da muhimmanci sosai. Sir McPherson, ba zai tava mantawa da wannan karramawa da Arewa ta yi masa ba. Za ta qara danqon zumunci tsakanin Qasar Ingila da Nijeriya ta Arewa. Irin wannan kara da karramawa, abubuwa ne da Turawan Mulki suka saba gani a Arewa. Hawan Ban girma, irin wannan ya samo asali ne tun a zamanin Gwamna Lugga.

Qasaitar wannan hawa da Sakkwato ta yiwa Sir McPherson ta isa abar alfahari, don tara dubban dawaki ba qaramin abu bane, musamman idan aka yi la'akari da yanayin wancan zamani na shekarar 1947. Ita wannan Daba sai ta zama

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 45

tambari a Nijeriya da qetare. Haka zalika, ana iya cewa ma ita ce ta yi sanadiyyar Dabar Sarauniya da aka yi a shekarar 1956.

Da zuwan wannan sabon gwamnan Nijeriya sai harkokin siyasa suka tashi haiqan, aka kuma shiga gina sabuwar Arewa. A wannan lokaci sai aka shawarta cewa Jihohin nan uku na Nijeriya, wato Jihar Arewa, da Jihar Gabas da Jihar Yamma, kowannensu ya sami Majalisar Dokoki takanta. A Arewa sai aka ce banda Majalisar Dokoki, ana so har a sami Majalisar Sarakuna. Daga nan Jihar Yamma ita ma ta kwaikwayi wannan ra a'yi, ta kafa Majalisar Sarakuna. Ta haka sai ya zama wakilai daga lardi lardi suna taruwa a Majalisa guda suna shawara. Wannan tsarin Mulkin Macpherson wanda aka faro shi daga shekarar 1951, sai ya kawo Tarayyar Nijeriya wadda ba kafaffiya sosai ba. Amma tsarin sai ya zama kamar shuka ne na ginin gama larduna har aka sami muhimmiyar jiha. Shirin ya taimaka don gama kai ya tabbata.

Kuma daga nan jiha jiha a zavi wakilai su tafi taro a Babbar Majalisar Nijeriya a Ikko. Ta haka, wannan shiri zai gama kan Nijeriya gaba xaya. Wannan shi ya zama Bismilla ga Arewa ta fara sanya bakinta da kanta, sosai a cikin Mulkin Nijeriya.[1] Wannan shiri ya baiwa Sarakuna wata dama da za su taka rawar gani a zamanin mulkin Dimukuraxiyya. Sun kuma taimaka wajen ganin gagarumin shirin ci gaban qasa na shekaru huxu, shekarar 1944 zuwa 1947 ya cimma nasara. Dalilin haka ne ya sa a shekarar 1945, 'yan Majalisar Dokoki ta Nijeriya, ta ba da iznin kashe fam miliyan hamsin da biyar a cikin shekaru goma masu zuwa. Waxannan kuxaxe, wata garavasa ce da Majalisar Ingila ta bayar, a bisa dokar taimakon qasashen da ke qarqashin mulkinta, wato dokar *Colonial Development and Welfare Act*.[2]

Ingantacciyar Siyasa

Wannan siysasa ce da ta haxa Sarakuna da Wakilai wajen cimma manufa wanda shi ne raya Nijeriya ta Arewa domin ciyar da ita gaba ta kowace harkar rayuwa. Da ingantacciyar Siyasa ce Sardauna ya yaqi ci ukun da suka ci Arewa. Da wannan Siyasar ce kuma aka cimma nasara wajen gagarumin Shirin Raya Qasa na shekara. Ita wannan Siyasa ta samo tushe ne daga zamanin Daular Usumaniyya. Ta farfaxo a zamanin Mulkin Mallaka, a Sigar Sarakuna a Siyasa. gwamnan Kaduna na taro da 'yan Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna akai-akai, a Gidan Shawara wato *Lugard Hall* wanda aka gina a shekarar 1948. Da farko da Sarakuna da 'yan Majalisar Wakilai a cikin *Lugard Hall* suke zama a lokuta daban-daban, kafin a gina na Majalisar Dokoki na Jihar Arewa a shekarar 1961. Babu shakka wannan taro ya kawo ci gaban Jihar Arewa. Saboda a lokacin

---

1 Abubakar Inan, *Auren Zobe*, shafi 30.

2 *Ibid*. shafi na 28

waxannan taruka ne ake tattauna ayyukan da za a aikata da kuma yin tsarin raya qasa domin samun ci gaba. An kuma sami ci gaba a kusan faxin jiha wato lungu da lungu lardi da lardi. Don kuwa babu Sarkin da zai yarda a bar lardinsa a baya. Wannan ya sa kowane Sarki zai nuna kishinsa na jama'arsa ne wajen nuna matsololin da ke addabar su da ganin an yi wani abu a kan waxannan matsololi.

Gwamna kan zauna da 'yan Majalisar Wakilai ko Majalisar Sarakuna ko kuma da dukkansu a lokacin da ya buqaci haka. Sarki goma zamani goma. An yi Gwamnoni daban-daban a lokuta daban-daban kowa ne Gwamna da irin salon shugabancinsa da kuma ayyukan da ya yi a lokakin mulkinsa. An yi Gwamnoni da yawa, amma za a kawo kaxan daga cikinsu da kuma yadda 'yan Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna suka taimaka wa mulkinsa. A wannan taron ne Gwamna ke karvar shawarwari Sarakuna da Wakilai da nuna ayyukan da ya yi a lokaci lokaci, ya taimaka wajen cin moriyar gumzar da aka samu, wato tallafin kuxi da aka samu daga Ingila wajen gyaran Arewa.

Shirin farko na tallafin bayan yaqi don gyaran Nijeriya ya fara aiki ne a ran 1 ga watan Afrilu na shekarar 1946. Wannan gumzar ita ce ta zama Basmilla ga sauran ayyukan da za a yi a nan gaba. An fara wannan muhimmin aiki a lokacin da Sir John Patterson KBE, CMG wanda shi ne Cif Kwamishina kuma gwamnan lardunan Arewa a shekarar (1943 – 1947). Wato a lokacin da yake dab da barin aiki. Ga abin da magajinsa Sir Eric W. Thompstone ya ce game da shi a shekarar 1947:

"Cikin shekaran nan mun yi sallama ta qarshe da Sir John Patterson K.B.E., C.M.G., wanda ya yi shekara talatin da biyu yana bautawa qasashen Arewa. Ya ba da kansa xungum ga ci gabanku da kyautatuwar zamanku. Mu kuma za mu yi alfarmar kwaikwayon qoqarinsa da qin kansa. In dai kuna iya gane yadda qasar nan take cikin shekarar 1915, a lokacin da ya sauka, ku gwada da yadda take yanzu, ina tsammani za ku gane, waxansu daga cikin abubuwan da su ke yanzu, da ba su a da, aikin Sir John Patterson ne. Saboda matuqar sabawa da sha'anin qasar nan, da zurfin qaunar da yake da ita ga qasar nan, lallai za a yi kewarsa. Ina fata shi da uwargidansa, Lady Patterson, su sami tsawon rai da murna a qasarsu."[1]

Qasar nan ta sha matuqar wahala a lokacin yaqin duniya na biyu. Nijeriya ta Arewa ta fi kowa ce jiha shan wahala, ta fi kuma kowa ce jiha ba da taimako wajen cimma nasara a lokacin wannan mummunan yaqi. Bayan an gama yaqi ne sai gwamnatin Ingila ta ware wasu maquxxan kuxaxe, waxanda ta bayar don raya qasashen da ke qarqashin mulkinta. Nijeriya na xaya daga cikin qasashen da suka

[1] AH/SNP/A3, Jawabin Mai girma Kyaftin E.W Thompstone, ran 4 ga Disamba 1947, shafi 5.

sami wannan tallafi don a raya qasa, a kuma bunqasa tattalin arziqi da jin daxin jama'a. Saboda haka sai aka yi muhimmin shirin raya qasa na shekara goma. Sarakunan Arewa sun sanya idanu wajen ganin Jihar Arewa ta amfana sosai daga wannan shiri, wanda ya zama babban harsashin gina Arewa da ci gabanta. Sir Eric, ya taka rawar gani wajen aiwatar da muhimman ayyuka a Arewa a qarqashin wannan shiri na raya qasa.

Shirin Raya Qasa Na Shekara Goma

Shirin Raya Qasa Na Asali, na 1946 zuwa 1956. Ga abubuwan da'aka shirya yi da kuxin kamar haka:

1	Samar da ruwan sha a qauyuka	£4,002,000
2	Samar da ruwan sha a birane	£4,060,000
3	Inganta Hanyoyi:	
	a) Giggina Hanyoyi	£5,581,000
	b) Kula da sabbin Hanyoyi	£1,465,300
4	Samar da wutar Lantarki	£1,544,200
5	Habaqa harkar Sadarwa	£820,000
6	Inganta Harkokin Sufuri a Teku:	
	a) Ma'aikatan Wucin gadi	£351,740
	b) Sabbin gine-gine	£624,200
	c) Sabbin na'urori da Jiragen ruwa	£2,542,000
7	Yaqi da Zazzabin cizon sauro a Ikko	£114,000
8	Harkokin Kiwon lafiya	£5,062,777
9	Yaqi da ciwon kuturta	£982,440
10	Bunqasa ba da	£4,058,470
11	Bunqasa ilimin sana'a	£1,115,453
12	Gudanar da Maxaba ar Hausa: Gaskiya Corporation	£152,350
13	Havaqa Aikin Gona	£1,823,700
14	Kula da lafiyan Dabbobi	£579,795
15	Kula da Gandun Daji	£826,136
16	Ciniki da Masana'antu	£120,000
17	Bunqasa Samun kifi	£156,830
18	Havaka Masaqun Garjajiya	£140,685
19	Qungiyoyin kula da jin daxin jama'a	£384,000
20	Tallafi don havaka ci gaban garuruwa da birane	£332,000
21	Bunqasa Ofisoshi	£895,000
22	Sashen Kididdiga	£100,000
23	Tsare-tsaren bunqasa gine-gine	£9,034,300
24	Ayyuka qan magance ciwon bacci	£469,070

25	Makarantar Horasda Ma'aikatan kula da Dabbobi	£101,950
26	Tsare-tsaren Havaka ci gaban qasa	£2,000,000

Wannan shiri ya haxa da ba da basussaka da kammala tsohon shirin da aka yi, a qarqashin raya qasa da jin daxin jama'a *Colonial Development and Welfare Act* na shekarar 1940. An sami jimillar kuxi fam miliyan hamsin da biyar (£55,000,000) wanda ya qunshi da fam miliyan ashirin da uku (£23,000,000) daga *Colonial Development and Welfare*, da fam miliyan goma sha-shida (£16,000,000) daga kuxin rance, da fam miliyan goma sha-shida (£16,000,000) daga kuxin shiga na Nijeriya.[1]

A cikin wannan shiri na Raya Qasa da jin daxin jama'a, akwai abubuwa da aka baiwa muhimmanci sosai, saboda haka aka zuba maqudan kuxi don aiwatar da su; kamar bunqasa gine-gine wajen ba da mahalli, da inganta hanyoyi da samar da isasshen ruwan sha a birni da qauye. Haka kuma bunqasa ilimi da kula da lafiya sun sami babban kaso. Wannan gawurtaccen shiri bai bar komai ba, hatta kula da bunqasa kamun kifi da masaqun gargajiya na masu kaxi da abawa, da koyar da sana'a an ba su muhimmanci.

An sake sabunta wannan shirin ci gaban qasa daga shekarar 1951 zuwa 1956. A wannan sabon tsarin ne zai ba da damar kammala wancan tsari na asali. A shirin akwai gudunmawar Nijeriya wajen yin wasu bincike wato "research." A jimillar kuxi fam miliyan talatin da huxu da dubu xari da tamanin da uku da xari shida da arba'in da xaya (£34,183,641) wanda ya qunshi fam miliyan goma sha-shida da dubu xari biyu da goma sha-biyu da xari biyar da tamanin da huxu (£16,212,584) tallafi daga *Colonial Development and Welfare Act*, da fam miliyan tara da dubu xari tara da hamsin da xari huxu da hamsin (£9,950,450) daga kuxin basussuka, da fam miliyan takwas da dubu ashirin da xari shida da bakwai (£8,020,607) daga kuxin shiga na Nijeriya.[2] Wannan sabon tsarin bambancinsa qadan ne da na asali wanda aka fara aiwatar da shirin daga ran 1 ga Afrilu 1946.

Wannan garavasar da aka samu daga qasar Ingila bayan qarshen yaqi duniya na Biyu ya taimaka gaya wajen gyaran Nijeriya. An kuma sami qarin kuxi don ba da tallafi ga Jami'ar Ibadan, da Kwalejin Al'adu, Kimiyya da Fasaha ta Nijeriya, da Gidan Watsa Labarai da *Geological Survey* da gyaran hanyoyi a qasar Kamaru, waxanda jimillarsu sun kusan fam miliyan uku da rabi, haka kuma an zuba maqudan kuxi wajen shirye-shirye a kan bincike wato "Research Schemes" waxanda ke da amfani wajen bunqasar ilimi da tattalin arziqi, da zaman lumana ga Nijeriya. Qasar Ingila ta ba da kuxi ne don a raya qasa, Sarakuna kuma sun taimaka wajen aiwatar da wannan shiri na raya qasa. Saboda wannan ita cewata

---

[1] *The Nigerian Handbook (1953)*, shafi na 72

[2] *Ibid.* shafi na 73

dama muhimmiya ta gina sabuwar qasar Arewa da Nijeriya baki xaya. A wannan lokaci Sarakuna ne kan gaba wajen bayar da muhimmiyar gudunmawa.

Wannan sabon shiri na raya qasa, sai ya zama harsashin shirye-shiryen Mulkin Nijeriya ba ki xaya. A wannan lokaci kuwa a na bin Tsarin Mulki wanda aka kafa Majalisar Dokoki don baiwa Gwamna Janar shawara game da Ikko da kewayanta, amma ana tafiyar da Mulkin Lardunan Arewa, yadda aka ce da su da azzimma ne na Gwamna.

Yana da amfani a fahimci waxannan shirye-shirye domin da su ne aka yi amfani wajen aiwatar da shirin raya qasa na shekara goma da kuma sauran ayyukan qasa har ya zuwa ga samun Mulkin kai. Samun wannan gumzar ne ya qara sanya Sarakuna shiga harkokin siyasa don su sa ido a gina Arewa. Ba Jihar da za ta so a bar ta baya. Qwamfa! Sai ga Sarakuna a Majalisarsu da 'yan Majalisar Wakilai na tafiya kafaxa da kafaxa wajen cimma manufa. Kowannensu kuma Gwamna na zama da su a wannan tafiyar ta Sarakuna a Siyasa. To, ta yaya hakan ya yiwu? Sardauna wanda shi ne wanda yaci gaba da aiwatar da shirin siyasa da Sarakuna, ya amsa wannan tambaya da bayani kamar haka:

> *Wata qila kuma za a so a yi tambaya a ce ya ya Sarakuna za su iya halartar irin taron nan, har wayau kuma su iya riqe harkokin qasashensu da ke can nisan mil da yawa daga Kaduna? Amsar da za a ba ka, ita ce ai ba kowane taro ne su ke halarta ba. Su kan halarci taro ne kurum, waxanda wajibi ne kowa da kowa ya zo. Ko kwanan gobe kuwa haka su ke yi. Taro na yau da kullum, a kan bi yan maganganu ne marasa nauyi, muhimman al'amuran kuwa a kan bar su sai an yi babban taro, sa'an nan a bi su. Wata wahalar, ita ce duk takardun ayyukan Majalisar, da Turanci ake buga su, a aikawa Sarakuna, waxanda sai sun bai wa yardaddun magatakardunsu su fassara masu abin da aka ce, kowane lokaci aka kawo takardun. "A taron farko da aka yi 'yan Majalisa sun zavi 'yan Majalisar da su ke so a tura su wakilci Arewa a Majalisar Dokoki ta Ikko. Aka zavi mutane 68 daga Majalisun nan biyu. Ta haka sai Sarakuna suka ga su ga Wakilin jama'a tasu, ga kuma Sarakunan Yarbawa. Ko da yake an yi 'yan gardandami game da sukar yin wannan abu, duk da haka al'amarin ya tafi sosai, babu wata tangarxa.*[1]

Wannan tsari na Sarakuna a siyasa ya tafi sosai, saboda dalilai guda biyu. Na farko, idan wajen siyasar mulkin jama'a ce Sarakuna ne kan gaba, don sun fi kowa gogewa akanta. Saboda an gina tsarin mulkinsu a kan harsashi mai inganci kuma

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi 91

tabbatacce. Dalili kuwa mulkin jama'a ba zai yiwu ba, sai da siyasa. Tsarin Sarakuna a siyasa yana da asali mai kyau saboda Sarkin Musulmi Muhammadu Bello ne ya kafa shi. Ya yi kuma kyakkyawan tasiri akan shugabancin Nijeriye ta Arewa, wadda take qasaitacciyar qasa ce mai bambancin da ban al'ajabi. A wannan zamani yanzu idan aka ce babu ruwan Sarakuna da siyasa to ance masu ne babu ruwanku da mulki, saboda wai sai "Xan Siyasa" ke siyasa. Wato shi ke mulki wannan yaudara da makala ce ta qara raba Sarakuna da jama'a don a zaizaye qarfinsu da tasirinsu, wanda tun farkon Siyasar farko har yanzu abin da a ke fafitikar yi ke nan. Ta haka ne za a ci nasara wajen raba jama'a da kyawawan xabi'u da tarboyyoyi waxanda su ne muhimmai. Amma har yanzu Sarakuna na nan da jama'arsu har kuma gobe. Haka zalika, an iya yin kambun-baka da cewa Arewa ba za ta sami shugabanci mai kyau da manufa ba, sai Sarakuna sun shiga harkar siyasa wato mulki, an damawa da su ba `yan kallo ba. Domin ta haka ne Arewa zata sami aiwatar da siyasa tabbatacciya.

Wato mulkin Jamhuriya illa ce ga Arewa. Don haka ne uban 'yan Siyasar Arewa M. Sa'adu Zungur ya zavarwa Arewa mulkin Mulukiya domin yasan illolin da ke qunshe a mulkin Jamhuriya. Babu wanda ya fahimci 'yan Kudu da niyyarsu ta mallake Nijeriya kamar M. Sa'adu Zungur, ya kuma yi matuqar qoqari wajen farkar da jama'arsa akan masifun da Arewa zata fuskanta in Nijeriya ta zama Jamhuriya. A waqarsa ta Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya, ya ce:

Za ku rera faxar da-na-sani
Da na bi jawabin Gaskiya

Allah Ya tsare ku faxar haka
Ya kiyaye Arewa gaba xaya!

Tutocin Shehu Mujaddadi
Daxa ba su zama Jamhuriya.[1]

Sarakuna su ne tutocin Shehu, mun ga matsayinsu samfurin wannan tsarin mulkin Jamhuriya. A yau xin nan masifun mulkin Jamhuriya ya addabi Arewa baki xaya ba abin kuma da 'yan Arewa ke yi sai fa "faxar da-na-sani." Domin kuwa mulkin da babu Tutocin Shehu Majaddadi wato Sarakuna, ai mulki ne da zai hallarkarda Arewa baki xaya. Domin kuwa ruwan da ya ci Tutocin Shehu Mujaddadi su ne suka ci malamai magada Shehu Mujaddadi. 'Yan Arewa za su koma bauta a cikin tsarin mulkin Jamhuriya, Malam Sa'adu Zungur ya tsinkayi aukuwar wannan hali yana cewa:

[1] A.M. Yakubu Sa'adu Zungur, shafi na 360

Babu shakka 'Yan Kudu za su hau
Dokin mulkin Najeriya

Su yi ta kau sukuwa bisa kanmu ko
Mu roqi zumuntar duniya

Matuqar yaranmu suna bara
Allah ba ku mu samu abin miya![1]

Duk da yawan 'yan Arewa a Nijeriya amma sai tasirin su ke dushewa matuqar gaske. Har ma yawansu ya zama tarin tsintsiya ne shirim ba shara! Saboda suna cikin tsarin mulki da ba 'Tutocin Shehu Mujaddadi, su da kariyar wato Majalisar Sarakuna sai ga masifu sun kewaye su ta ko'ina don sun rasa kariya da garkuwar Sarakuna. M. Sa'adu zungur ya gargadi 'yan Arewa da su gujewa mulkin Jamhuriya su rungumi mulkin Mulukiya, duk da cewa anfi kambama mulkin Jamhuriya a wancan zamani. To, idan kunne yaji, jiki ya tsira. Saboda limamin siyasa a Arewa, ya ce:

Duk misalan nan nar Amirka ba
Mai kyau, na shirin Jamhuriya

Kar ku ruxu da zancen ja'irai
Masu son halakar Najeriya

Gaskiya ba ta neman ado
Ko na daxin muryar zabiya

Karya ce mai launi bakwai
Ga fari da baqi ga rawaya

Ga shuxi ga kuma algashi
Toka-toka da ja sun garwaya

Ba ta 'ya 'ya sai ko tai fure
Sai rassa sun fi dubu xaya

[1] A.M. Yakubu Sa'adu Zungur, shafi na 362

'Yan Arewa ku daina gaganiya
Ku riqe daular ku da gaskiya.[1]

Tsarin mulkin Mulukiya wanda yake da Sarakuna a Siyasa shi ne tsarin mulkin Gaskiya wadda "ba ta neman ado." Wannan tsari ne kuma da zai haifar da siyasa ingantacciya. Amma wannan tsari ne da 'yan Kudu kewa naushi da tokari, saboda basu da Sarakuna, musamman 'yan Jihar Gabas wadda jam'iyyarsu ta NCNC ta fito tana kambama tsarin qarya wato Jamhuriya wadda "ba ta 'ya'ya sai ko tai fure." Domin idan da Majalisar Sarakuna babu yadda "yan Kudu za su hau dokin mulkin Nijeriya. 'Yan Kudu sun sami galabar mulkin Nijeriya ta wannan mulkin Jamhuriya ba za su taba yadda dana mulukiya ba. Wata illa da tsarin mulkin Jamhuriya ta haddasa wa 'yan Arewa shi ne ya kashe musu kishin kansu saboda sun yi watsi da Tutocin Shehu Mujaddadi. Muna ga irin wannan rashin kishi wajen wofintar da Makarantun Allo da miliyoyin xalibansu da aka yi a wannan zamani. Don haka ne Malam Sa'adu Zungur ya ce: "Kai Bahaushe ba shi da zuciya, za ya sha kunya nan duniya!"

Dalili na biyu shi ne tsarin Mulkin En'e ya kafu sosai ya kuma tasirantu a kan jama'ar Arewa. Don kuwa farkonsa da adalci ya taso, daga qarshe ne ya rusuna qasa saboda zalunci. Mulkin En'e shi ne tsarin da ke kaiwa ga kowane lungu na jama'a a qasar Hausa. Wato ya kusantar da jama'a ga shugabanninsu. Tsarin mulki daga Sarakuna zuwa ga Hakimai da Dagatai da masu Unguwanni har yanzu shi ake bi akai ga jama'a, musamman idan ana son a aiwatar da ayyukan ci gaba ko kuma kwantar da tarzoma.

A lokacin da Mulkin En'e ke tashe, shi ne ya kawo ci gaban qasa da rayuwar jama'ar Arewa. Ya kuma taimaka gaya wajen gyaran Nijeriya ta Arewa tun kafin 'yan siyasa su shigo fagen mulki, su zo da babakere da handama. Mulkin 'yan Siyasa bai haifar wa da Arewa xa mai ido ba, sai ya maida su qyale-qyale huhun-ma'ahu. Hasali ma dai, tun da aka raba Sarakuna da siyasa sai Arewa ta komafifa-iya-koma-baya.

Turawa sun zo suna mulkin Arewa takan Sarakuna. A kuma wannan tsari suna taka rawar gani wajen tafiyar da mulkin wannan qasa, ta siyasa mai wuyar gaske. A wannan zamani Sarakuna na tsaka mai wuya. Idan suka yi sakwa-sakwa Turawan Mulki su matsa iko har talakawa su vara. Idan kuma suka matsa sosai, sai Turawan Mulki su vara da cewa suna bauxewa alqawarin tsarin mulki da aka yi da yarjejeniyar da ake bi. Haka dai Sarakuna suka riqa yin taka tsantsan, wajen ganin Turawa sun gina Arewa ba a kuma bar ta a baya ba. Bin wannan siraxi a wannan mawuya cin lokaci, shi ne wani matsayi mafi wuya da Sarakuna suka sami kansu a ciki. In banda lokacin da Turawa suka angije Daular Usumaniyya a

[1] A.M. Yakubu Sa'adu Zungur, shafi na 358

shekarar 1903, Sarakuna ba su shiga lokaci mai haxari kamar wannan zamani ba. An ba su gadin akuya guda ga kuraye biyar kewaye!

Ko da yake mulkin *Indirect Rule* ya kawo wata harqiya a mulkin Sarakuna, amma sun nuna qwarewar mulki da sanin makamar mulki wanda ya ba Turawa sha'awa. Tsarin mulkin En'e da su ke jagora sai ya zama abin koyi ga sauran jihoji.

A shekarar 1919, Oba Obaseki na Benin ya zo lardin Zazzau wajen gogaggun Sarakunanta don ya koyi sha'anin mulki. Saboda ganin tsarin mulkin En'e na tafiya sosai a Arewa, sai aka nemi a faxaxa shi zuwa sauran jihohin wannan qasa. Ganin haka ne ya sa Turawan mulki suka gabatar da shi a Kudu da Yammacin Nijeriya. A wannan salon mulki Sarakuna ke jagorar Majalisarsu ta En'e tare da sa idon Ofisoshin Mulki, waxanda za su tabbartar da ganin mulkin ya tafi a kan tsari an kuma rage zaluncin jama'a, abin da ake qorafin Sarakuna na aikatawa. A duk ayyukan gwamnati ta kansu a ke aiwatarwa. Haka kuma En'e ke da alhakkin karvar kuxin haraji, da tafiyar da kotuna da kasuwanni da raba filaye da makamantansu. Dalilin haka ne tsarin mulkin ya yi baqin jini ga `yan adawa, ya kuma sadu da mummunar suka daga 'Yan Siyasa.

Duk da haka mulkin En'e ya samu karvuwa sosai. An ci gaba da aiwatar da wannan tsari a cikin qabilun arna marasa addini, bayan an yi nazari da irin al'adunsu. A hankali sai aka gabatar da tsarin mulkin En'e a lardunan da ke Kudanci Nijeriya. An fara aiwatar da shi a garin Abeokuta, da Oyo, da Ijebu da Ondo, waxanda suke a lardunan Yammacin Nijeriya. An kuma gabatarda shi a lardunan Benin a shekarar 1919 zuwa 1922. An kai shi qasar Kamaru a shekarar 1921. Amma sai a shekarar 1928 mulkin En'e ya samu shiga lardunan Gabas. Amma an samu matsala sosai wajen gabatar da mulkin En'e a lardunan Gabas, saboda rashin samun tsarin shugabanci da ya dace da shi. Domin babu tsarin shugabanci irin na Arewa ko lardunan Yammacin Nijeriya. A lardunan Gabas, a na mulki ne ta jagorancin dattawa na qauyuka a kan tsatsonsu.[1] Saboda haka 'yan wannan lardi ba za su so tsarin mulkin Mulukiya ba domin basu da gidajen Sarautar gargajiya.

Sardauna Ahmadu jagoran mulkin Siyasa da Sarakuna ya sha suka daga mahassada da 'yan adawa. An zargi wannan tsari da nawa da tafiyar hawainiya. Da jaridu da jam'iyyun mulki suka ta yin surutai suna neman tasa qeyar wannan Jiha don ta yi aikin hanzarin da zai haifar da nawa, sai Firimiya ya basu amsa da cewa:"Mu fa mutanen Arewa, mutane ne waxanda suka san kansu, ba za mu yarda a riqa tunkuxa mu kamar bayi ba." Ya qara da cewa, waxansu mutane na

[1] *Nigeria Handbook*, shafi na 53

sauran Jihohi da Ikko suna cewa tafiyar Arewa ta cika laqaqi.[1] Don kuwa 'Yan Kudu maqiyan Tutocin Shehu Mujaddadi ne ainun.

Duk da haka da Tutocin Shehu Mujaddadi, Sardauna ya mulki Arewa, ya bata kyakkyawan jagorancin da ya ciyar da wannan Jiha gaba. Babu kuma inda waxannan Sarakuna ke samun mummunar hasada da qiyayya kamar Ikko da sauran jihohi, waxanda suka zaqe wajen kai masu naushi da tokari. Amma Sardauna da yake gwanin mulki ne sai ya ci gaba da jagorancin Arewa sannu a hankali. Ya kuma baiwa 'yan adawa amsa da cewa, " Na yarda da wannan. Amma ina so in shaida muku Jihar Arewa ba za ta yarda da irin hanzarin da jihohin nan biyu su ke yi ba, sai in ta ga jama'arta na buqatar Haka nan."[2]

A zamanin mulkin Sarakuna a Siyasa ne, Arewa ta samu ci gaban da ya baiwa kowa mamaki da ban al'ajabi. Firimiya Sir Ahmadu Bello ne ya bayyana haka yana mai farin ciki da alfahari, ya ce:

> *Yau wajen shekara 30 ke nan tun da mutanen Kudu suka fara zuwa qetaren ruwa neman ilimi a Ingila Amirka da sauran qasashe, sun koyi abubuwa da yawa, harda na mulki. Sun dawo suna shugabancin mutanensu. Babu wani cikin Samarimmu da ya fara leqa qasashen duniya, sai bayan babban yaqin nan na duniya.*
>
> *A cikin shekarar 1946 aka samu 'yan Arewa a Majalisar Nijeriya, alhali kuwa tsarin mulki na shekarar 1922 sai da ya kawo har farkon yaqin shekarar 1939 zuwa 1945. Turawa da mutanen Kudu ke mahawara kan sha'anin kuxaxen gwamnatin Arewa. Cikin shekarar 1946 aka kafa Majalisar Wakilai da ta Sarakuna sosai a Arewa. Amma duk da haka sai wajen qarshen shekarar 1951 aka soma samun Jam'iyyoyin mulki a Arewa. A wannan shekarar NPC ta zama Jam'iyyar mulki, gama cikin shekarar 1950, sa'ad da aka yi Taron Ibadan na Gyaran Mulki, Jam'iyyar Kyautata zaman jama'a ce kurum. "Idan ana kwatanta yawan ci gaba a sha'anin mulkii tsakanin Kudu da Arewa, sai a duba babban ci gaban da Arewa ta yi cikin shekara biyar kurum da wanda Kudu ta yi cikin shekara talatin.*[3]

Tirkashi! Wannan ya nuna cewa ci gaban da tsarin mulki na Sarakuna a Siyasa da Sardauna ya jagoranta na shekara biyar kacal, dai-dai yake da ci gaban Kudu na shekara talatin! Sarakuna a lokacin da suka dulmuya ka'in da na'in a

---

1 GTK, Ta 730, 4/9/1956

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*, 730, shafi na 5

siyasa sai Arewa ta kai ga ci gaba wanda ba kamarsa a Nijeriya. Saboda haka ana iya cewa sirrin ci gaban Arewa da Sardauna ya kawo wa Arewa na, Sarakuna ne. A dalilin haka ne Firimiya ke cewa babu yadda za a yi gwamnatinsa ta kai ga qasaitaccen ciyar da Arewa ba tare da Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai ba. Da fuka-fukan waxannan majalisu ne jirgin Arewa ya ta shi sama. Arewa sai ta faxi qasa war was da aka fige Majalisar Sarakuna bayan rasuwar Sardauna. Qaddara ta riga fata. Abubuwan da M. Sa'adu Zungur ke guje wa Arewa, sun same ta.

Idan sha'anin gogewa wajen mulki ne, Arewa ke kan gaba a tarihin wannan qasa. Sarakunan wannan qasa ba iyayen al'umma ba ne kawai, waxanda ba su da katavus a harkokin mulkin jama'a, a'a su ne shugabanin jama'a na asali waxanda, za su iya ba da mulki mai kyau da xorewa a duk wani zamani, na yanzu ko kuma wanda zai zo gobe. Shika-shikan mulki ba sa sauyawa, sai dai tsarin yadda aka kafa mulki ko yadda ake tafiyar da shi su sauya. Sir Ahmadu Bello ya bayyana su: "Maqasudanmu masu sauqi ne qwarai. A sami kyautata halin zaman lafiya, da kiyaye dokoki, da zama cikin halin abokantaka, tsakanin sauran jama'armu; a yi mulki ta hanya mafi kyau da rashin nuna son zuciya; kowa da kowa ya sami 'yancin yin addini da tunani irin yadda ya ga dama; a aikatawa kowa alheri.[1]

To, waxannan kaxan ne daga cikin ayyukan ci gaban al'umma da Sarakuna ke yi, kafin al'ammura su dagule. Har yanzu waxannan ayyukan su ke yi. A mulkin Turawa a kuma maganar da ake yi a kanta yanzu, Sarakuna 'yan Siyasa ne kuma shugabanni na qwarai. Kusan duk laifukan da 'yan siyasa masu mulki suka zargi Sarakuna da su, to, ga shi yanzu, suna tafka zalunci da rashawa fiye da kima, waxanda suka maida na Sarakuna kamar kwabo a cikin aljihu. Ai laifi tudu ne, sai ka tsallake naka, ka hango na wani. To, kafin a ce komai sai aga irin rawar da Majalisar Sarakuna ta taka wajen gina harsashin ci gaban Arewa, musamman a lokacin da ake aiwatar da shirin raya qasa da zaman lafiyar al'umma. Sir Bryan, ya yi wani tsokaci akan al'adar Sarakunan Arewa, inda ya ce:

"A da ma har Sarakuna kan tara talakawa wajen aikin gayya, ko su gyara hanyoyi, ko su gyara bariki, ko makaranta, ko ma gidajen Sarakuna ko masu yi masu noma a gonakinsu. A sakamakon wannan, shi mai gari sai ya shirya abinci, masaki-masaki, a ba mutanen nan. Waxansu ma ya basu kuxi. Shi kuma a lokacin rashin lafiya, ko yunwa, ba ya da gindin zama. Sai ka ganshi kumar uba wanda masifa ta faxa wa 'ya'yansa."[2]

---

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi 92

[2] Abubakar Imam, *Auren Zobe*: *Abutar Nijeriya d Ingila*, shafi na 23

Sarakunan Arewa da ma al'adarsu ce, mulki da kishin jama'arsu. Sun kuma daxe suna sa ido wajen ci gaban al'ummarsu. Ko da aka samu gumzar kuxi wajen gyaran Nijeriya, sai suka tashi kai tsaye suka kuma himmatu wajen ganin an kawo wa qasarsu abubuwan ci gaba. Babu wanda ya zarge su da son kansu ko kuma rashin kishin jama'arsu a wannan zamani na Sarakuna a siyasa. Sarakuna sun kevanta da jagoranci da kishin jama'arsu. Duk waxannan alamomi ne da ke nuna mulkin Mulukiya ne ya dace da Arewa. Babban masifar da ka faxawa al'umma, ita ce shugabanni su yi mulkin jama'a ba tare da kishin jama'arsu ba. Mulkin Dimukuraxiyya, mulki ne na rashawa da ke danne talaka saboda yana assasa tasirin jari hujja akan al'umma, dalilin haka mulkin siyasa ke tafiya da rashin kishin jama'a, musamman a tsarin mulkin Jamhuriya, wanda aka fi tallatawa jama'a. Siyasar manyan qasashen Turai da Amirka da rashawa ake tafiyar da da ita tare da zaluncin qasashe masu tasowa. Akan harsashin da da Sarakuna da Gwamnonin mulki su ka gina, su ka kuma yi gini mai kyau da qarfi da qarko Arewa ta ginu sosai a cikin hanzari. Saboda haka sai ace, "'Yan Arewa ku daina gaganiya, ku riqe daular ku da gaskiya." Domin kafa ingantacciyar Siyasa wadda za ta yaqi Ci Uku da ke cin Arewa.

Matsalolin Majalisar Siyasa

Idan aka yi nazarin jawabin da Wakilin Bauci M. Abubakar Tafawa Valewa ya yi a Majalisar, Wakilai a zamanta na farko a shekarar 1947 za a fahimci cewa akwai adawa a tsakanin Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna. Akwai kuma takun saqa a tsakaninsu. Firimiya ya fahimci wannan hali wanda ba hamayyar siyasa ce ba, a'a, 'yan Majalisar Wakilai suna neman su ga bayan Majalisar Sarakuna ne, amma ba za su iya fitowa fili su nuna maitar su a fili ba, saboda Sarakuna nada qarfi sosai, domin talakawa suna bayansu Turawan Mulki kuma ba su fara juya masu baya ba. Suna kuma ganin idan siyasa za a yi, to, ai zavavvun Wakilai sun fi Wakilai na Sarautar gargajiya. Wato dai an fara karkata alqiblar Arewa zuwa ga tsarin jamhuriya.

Firimiya ya bayyana matsololin waxannan Majalisu guda biyu. Ana iya samun Majalisar Wakilai mara kyau wadda in haka ya faru za a sami matsololi masu yawa. Sardauna ya bayyana cewa: "To, idan Majalisar ce fa ba ta da kyau, me za ka iya yi? Muna kuwa da irinsu da dama. Idan jama'a ne suka zave su, abin ma ya fi cin rai. A qarshe dai ba abin yi sai a dakatar da su kurum. Amma dai-dai wane lokaci ne ya kamata a dakad da su xin?"[1]

Kyawon 'yan Majalisa wajen adalci da son raya jama'a ne abin dubawa, ba Majalisar ba xungum. Idan jama'a suka zavi tumun-dare ko kuma waxansu suka murxe zave, suka zama 'yan Majalisa ta varauniyar hanya ba yadda za a yi

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 109

wannan Majalisa ta haifi xa mai ido. Idan haka bai auku, ba a na iya samun matsololi ta wata hanya dabam kamar yadda Firimiya ya bayyana kamar haka:

> *Ga kuma wani bala'in ya kunno kai. A lokacin da ake yin zave don shiga wannan Majalisa sai wani qarfi ya tattaru a wurin. Aka mamaye jam'iyya guda, xayar kuwa ta farka, ta zabura, ta jefa quri'a. Sai mai kaxan xin nan ta sami sa mabiyanta duka majalisar ba a sami abokan hamayya da za su riqa kushe al'amura a ciki ba. Amma don tsananin rashin dacewar waxanda aka zava xin nan, to, ko akwai 'yan hamayya a ciki ma, ba za a sami wani bambanci sosai ba. Ba safai kuwa irin wannan ke aukuwa ba, amma dai ba baqon abu ne ga waxansu irin Majalisun ba.*
>
> *Wata irin wahalar kuma takan vullo ne a wata hanya dabam. 'yan Majalisar da aka zava, su kan sauka ne daga muqaminsu bayan shekara uku. Sai a sake zave, in an gama sai ka ga daga cikin waxancan tsofaffin 'yan Majalisar, ba a sake zavo ko xaya ba. An sami sabuwar Majalisa ke nan. Ban da ma ba su da sanannan ciki game da yadda a ke tafiyar da sha'anin Majalisa, suna ma cike da jahilcin rashin sanin abin da wancan Majalisar ta da ta aikata. Sai kuma su shiga soke duk hikimomi, su yi ta qin goyon bayan al'amarran da aka riga aka yarda da su tun shekara uku da suka wuce, waxanda aka ajiye waje xaya bayan an tafka mahawara mai tsawo kansu. Vata lokacin ya kai inda ya kai.*[1]

Sauye-sauyen 'yan Majalisa a lokutan zave daban-daban ya kan haifar da tufka da warwara a harkokin ci gaban jama'a a siyasa. Saboda haka sai ci gaban jama'a ya riqa tafiyar kura. Irin wannan hali ne ya rikirkita jama'a, ya kuma cunkusa masu ra'ayin son canji da sauye-sauye da mummunar aqidar "ku ci mu ci." Wato idan wani rukuni na jama'a na kan mulki, sai shugabanni da mabiyansu su yi amfani da wannan dama"su ci" su azurta kansu kafin a sauya su. Saboda sai haka sai wannan kuma ya haifar da aqidar gafiya tsere da na bakinki. Haka kuma tsoron za a sauya shugaba da gaggawa, sai ya sa shi xaukar duk wani matakin da zai dawwama a mulki ko kuma ya qara wa kansa wasu shekaru a kan gadon mulki. A wannan zamani, kuma saboda haka ne ma aqidar "Ta zarce" ta hudo kai ta assasa tafka maguxi a wajen zave da kashe-kashe a wajen neman nasara ta kowane hali ta kuma ko qaqa. Ire-iren waxannan matsaloli ne suka wofintar da mulkin Dimukaraxiyya a Nijeriya ta Arewa. Mulkin Dimukuraxiyya kuwa ba shi yiwuwa sai da sauye-sauye da kuma hamayya. A qasashe masu tasowa kamar

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 109-110

Nijeriya a Siyasa tana haddasa varaka a harkokin zamantakewar jama'a saboda ba safai ake duba xan Siyasa ta fuskar shugabanci ba, a'a, an fi dubansa da tabaron addini ko qabilarsa. A rikice-rikicen addini da qabilanci waxanda hamayyar siyasarta haddasa. Ga wani misalin sauyi a siyasar farko.

Ranar da kowa yake jira a Nijeriya, da Kamaru, da Ingila wataqila ma da waxansu qasashen na duniya ta zo. Ita ce ranar 1 ga Satumban shekarar 1956, ranar da aka rushe Majalisar Wakilan Jihar Arewa, domin a sake zave. A cikin qa'idodin zaven nan da za a yi, an cewakilai goma sha-tara (19) daga cikin xari da talatin da xaya (131) za a zave su ne ta hanyar zave falan xaya. A ko'ina da ina da za a yi irin wannan zave na falan xaya, ran 15 ga Nuwamba, za a yi shi a qare.

Sauran wakilai xari da goma sha-biyu (112) kuwa, waxanda za a yi zavensu ta hanyar matakan zave biyu ko'uku, za a qare zavensu duka a ran 30 ga Nuwamba, wataqila ma kafin ran nan za a gama yawan wakilan da za a naxa.

Majalisar Sarakunan Arewa ita ma a wannan ranar aka rushe ta. Ita ma za a qara yawan Sarakunan da za su shiga cikinta, domin a samu qarin Sarakuna masu daraja ta uku, wataqila ma har da ta huxu, su shiga. Dalilin wannan shi ne domin akwai waxansu 'yan wurare da su ke jin kamar ana wulaqanta su, domin Sarakunansu ba su cikin Majalisar Sarakuna.

gwamnatin Jihar Arewa ta buga sabbin dokokin zave. An cewaxannan sabbin qa'idodi an shirya su a bisa shawarwarin da wata kwamiti ta bayar, wadda aka naxa cikin shekarar 1953, domin ta tsaro wa Jihar Arewa hanyar zaven wakilai, wadda za ta dace. Amma kuma ba da shawarwarin kwamitin nan kaxai aka dogara ba. An dubi irin tafiyar da zamani ya yi, daga shekarar 1953 zuwa yanzu 1956, an dai-daita tsarin.

Ba a kau da ji ba daga soke-soken da jama'a suka riqa yi wa qa'idodin zave na shekarar 1951 ba. An dube su. Waxannan shawarwari na kwamiti, an kai su gaban Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna, an yi mahawara kansu, kafin a yarda da abubuwan da aka yarda da su. Har ila yau, a cikin muhimman qa'idodin zaven nan, dukkan waxanda za su yi quri'a, lallai ne su zama maza ne, waxanda suka biya harajinsu. An ce a dukkan kowane wurin zave guda, wakili xaya za a zava. Ga lissafin wuraren da za a zavi waxansu daga cikin wakilansu a hanyar zave falan xaya.

Kano, wakilai huxu, da Sakkwato, wakilai biyu, da Yerwa, wakilai biyu, da Gusau, wakili guda, da Qaura Namoda, wakili guda, da Katsina, wakili guda, da Nguru, wakili guda, da Ilorin, wakili guda, da Offa, wakili guda, da Bida, wakili guda, da Jos, wakili guda, da Okene, wakili guda, da Zariya, wakili guda, da Kaduna, wakili guda.

Zaven da za a yi a sauran wurare, ban da waxanda aka ambata xin nan, za a yi shi a bisa matakin zave ne. a yawancin wurare, matakai biyu ne kurum. Qurio'in

da za a yi a zave na mataki na qarshe, da waxanda za a yi wuraren da aka yi rajista a asirce za a yi.[1]

A wajen yin zave akan shimfixa qa'idoji masu yawa waxanda ke ba da damar soke xan takara komai dacewarsa. Su kuma waxannan qa'idoji ba safai ake cika su ba, a kan nuna son rai da tufka almundahana wajen tantance xan takara. A wani lokaci kuma a kan kayad da xan takara mafi dacewa saboda haka waxanda jama'a ke so ba shi za su samu ba.

Idan aka yi nazari sosai sai aga wannan tsarin zave da sake zave suna ba da damar tafka maguxi da kawo tashin hankali. A duk lokacin zave, sai an yi kashe-kashe da asarar dukiya mai tarin ximbin yawa. Haka mulkin Dimuquradiyake haifarwa ba Nijeriya ba a sauran qasashen duniya, musamman qasashe masu Tasowa. Kai har ma qasashen Turai da Amurka mulkin Dimukuraxiyya ya zamar masu alaqaqai. Jama'ar waxannan qasashe a kullum zanga-zanga suke yi saboda katsalolin zave da qorafe-qorafe waxanda ake samu ko yaushe.

A wannan lokaci kuma ake samun qaraku masu dama a kotunan sauraren qararrakin zave, saboda hankalin 'yan siyasa da jam'iyyunsu sun shagala wajen sun tabbata su ci zavuka sun kuma kare waxanda su ka ci zave. Saboda haka ba safai suke da isasshen lokacin yin ayyukan ci gaba ga jama'a ba. A kan kashe dukiyar talakawa wajen kai qara da xaukaka qara waxanda ke xaukar lokaci mai tsawo misalin shekaru biyu ko uku. Sauran 'yan watanni ko shekarun da suka rage, to, ba abin yi sai fafitikar yadda za a ci zaven dake tafe ake fuskanta. A dalilin haka ne ba samun isashen lokacin da za a yi wa jama'a aikin da zai ciyar da su gaba.

Irin mulkin siyasa ke nan sai dai kowace qasa ta yi mulki yadda ya dace da addini da al'adun jama'arta. A zaman siyasar farko an haxa siyasa da mulkin gargajya aka murje su don su tafi da zamani. Arewa na bin tsarin mulkin Mulukiya ne irin na qasar Ingila. An ga amfanin yin haka a wannan zamani.

Tsarin siyasar mulkin Dimukuraxiyya yana da nasa matsalolin, ba tsari bane da yake kammalallai wanda zai warkar da matsalolin jama'a ya kuma basu wadata tare da zaman lafiya. Har yanzu babu wata qasa da ta gamsu da mulkin Dimukuraxiyya musamman a wannan zamani. A yawancin qasashe da ke bin wannan tsari a Turai, da Asiya da Afirka suna fama da matsalolin tavarvArewar arziqin qasashensu da tarzoma har ma da kashe-kashen jama'a tare da varnar dukiyoyi masu yawa.

Masana da yawa sun aibanta tsarin mulkin Dimukuraxiyya domin illarsa a kan tattalin arziqin qasa shi ne mafi muni. Saboda haka rashawa da wannan tsarin mulki kamar hanta da jini ne, ba a raba su. A dalilin haka ne kuma ya kamala

[1] GTK 4 ga Satumba, 1956

kowace qasa da ta qirqiro wa kanta irin samfurin Dimukuraxiyya da ya dace da al'adunta, da arziqinta. Don kuwa bin Dimukuraxiyyar Turai sau da qafa, halaka ne. Kamar yadda gara ke cin katako haka wannan tsari ke cin tattalin arziqin qasa saboda yana kau da kishin jama'a ga shugabanni ya kuma assasa darajar abin duniya bisa kan mutane.

A farkon shigowar siyasa wannan qasa. Sir Ahmadu Bello ya yi qoqarin nuna wa jama'a matsalolin da siyasar ke da su, domin su yi hattara, kada su yi watsi da al'adunsu wajen tafiya da zamani. Kamar yadda M. Sa'adu Zungur ya gargaxe su.

Ko da yake tsarin mulkin na iqirari da cewa mulki ne wanda jama'a suka kafa, amma talaka bai amfana da shi ba saboda mulki ne da jari da hujja ke tafiyar da shi. A wannan tsari kowa na da 'yancin jefa quri'a. Da yawan qarin ake rinjaye ba sahihancin waxanda suka jefa quri'un ba. A tsarin siyasar farko, tsari ne na Falimantare, samfurin qasar Ingila. Kuma tsari ne na Mulukiya. A wannan tsari, jam'iyyar da tafi samun yawan kujeru a Falimantare, ita ce zata kafa gwamnati, saura kuma suka jam'iyyar 'yan adawa.

Waxanda ba su yi rinjaye da yawan kujeru ba wato *minority*, suna da haqqin yin adawa da gwamnati, wanda shi ne yake xaya daga cikin manyan shika-shikan Dimukuraxiyya, sauran kuwa su ne damar da masu rinjaye ke da shi wajen kafa gwamnati, da haqqin xan qasa na jefa quri'arsa. Tun da tsarin mulki ne da yake kawo talauci saboda haka sai aqida ta mutu murus. A dalilin haka ake sayen 'yan adawa domin masu rinjaye su ci karen su babu babbaka.

A tsarin Dimukuraxiyya irin na Ingila, minority basu tashi a tutar banza domin suna da damar yin adawa da gwamnati a Majalisa, inda aka sansu da sunan Masu Adawar Mai Alfarma, wato *Her Majesty's Opposition*. Shugabansu kuma yana da albashi na musamman. Shi kuma Shugaban masu rinjaye wato *Majotity* shi ne Firayim Minista. Amma ba safai ake yin haka a qasashe masu tasowa ba, inda talauci ya yi wa jama'a katutu. A waxannan qasashe an an xauki adawa a matsayin 'faxi' ne da gwamnati. Saboda haka in xan adawa ya tsaya kan aqidarsa ta siyasa sai a kashe shi. In kuma ba shi da aqida sai a saye shi wurin na gugar wuri.

Ana iya cewa shi Firayim-Minista tunda shi ne Shugaban masu Rinjaye a Majalisa, yana iya yin yadda yake so a wajen zartar da shirin doka. Haka nan ya kan faru, sai dai in an samu qwararrun 'yan Adawa, waxanda ka iya sa gwamnati yin taka-tsan-tsan, domin suna iya sawa ayi wa doka gyaran fuska kafin Majalisa ta karva. Amma hakan ba zai yiwu a kashe masu tasowa ba.

Saboda an xauki adawa faxa ne da gwamnati ita kuma Hukuma ce mai son yin abinda taso. Duk kuma wanda ya ja da ita zai xanxana kuxarsa. Idan aka kafa dokar masu Rinjaye za su kafa gwamnati, sauran kuma su zama 'yan Adawa saboda haka sai a kafa qungiyoyi da za su riqa yin adawa da manufofin gwamnati don a kyautata wa jama'a. To, me zai faru in an qurmushe 'yan adawa.

A Ingila, tsarin jam'iyyoyi ya faro ne daga qarshen qarni na goma sha-bakwai, inda aka shirya shi zuwa jam'iyyar 'yan "Conservatives" wato masu ra'ayin mazan jiya da 'yan "Liberals," masu sassaucin-ra'ayi.

A irin wannan tsari za ka iske hamayya a siyasa, inda masu adawa za su riqa yin tir da ayyukan gwamnati a akasarin lokaci don son yin suna suke vata gwamnati. A Dimukuraxiyyar Falimantare (Kalmar Faransanci da ke ma'anar, "magana") ta vullo ne saboda la'akari da aka yi da kada a bar Sarki ya samu muxlaqin mulki wajen kafa dokoki, sai da amincewar 'yan Majalisa. Tun daga wancan zamani tsarin Falimantare na Ingilishi - shi ne uwar dukkan Falimantarori.

Amma duk da haka mulki a tsarin Falimantare na hannun Ministoci ne waxanda suke su ne masu rinjaye a Majalisa. Su kan sha suka ne da tambayoyi kowane lokaci, don ta haka ne ake tafiyar da adawa.

Haka kuma manyan Ministoci ke da qarfin riqe komai a hannunsu, su ne suke da shawarwari tsara gwamnati. Su ne kuma ke da shawarwari tsara manufofin gwamnati. Su ne kuma ke riqe da ragamar mulkin dukkan hukumomin gwamnati waxanda ke da ma'aikata ba tare da bambancin jam'iyyar da suka fito ba.

Ta haka ne tsarin Dimukuraxiyyar Ingilishi ta bambanta da ta Amurka, inda kowane jami'i na iya rasa aikinsa matuqar jam'iyyarsa ta rasa mulki.

Mulkin Dimukuraxiyya shi zamani ya zo da shi, an ce zamani riga. Akwai wasu salon mulki iri uku, Mulkin Kama-Karya, shi ake kira *Autocracy*. A wannan tsarin mulki, ikon komai na ga hannun mutum guda. Irin mulki ne da Hitler na qasar Jamus da Mussolini na Italiya da Tsar na qasar Rasha suka aiwatar a qashashensu. Akwai tsarin mulki sanfurin *Oligarchy*, a inda 'yan tsiraru za su yi qarfi su riqe ikon komai a hannunsu. A mulkin *Aristocracy* kuwa, iko na hannun masu Sarauta waxanda su ne ke da mulki su ne kuma suka gadar da mulki ga 'ya'yansu. Wannan tsari ne na Mulukiya.

A tsarin Jamhuri kuwa babu sarauta, mulki na hannun zavavvun Wakilai. M. Sa'adu Zungur ya kushe mulkin Jamhuriya a waxarsa. Ya ce:

Wa'azi ne mulkin Indiya
Da ta zam daular Jamhuriya

Yau ina manya na Sarakunan
Pakistan ko kuma Indiya?

Da Nizam, Maharaja da Raja duk
Sai kuka ba mai dariya

Da Sarakai sun fi xari biyar

Duka sun watse ba ko xaya

Sai ka ce fa daxai ba a yi su ba
Kunji sharrorin Jamhuriya[1]

duniya ta gwada mulkin *Autocracy*, da *Oligarchy* da *Aristocracy*, amma tana yayin mulkin *Democracy* a yanzu. Amma duk waxannnan salolin mulki, an aibanta su saboda suna da naqasu. Salon mulkin Islama ne duniya bata jarraba shi yadda ya kamata ba saboda akwai hamayyar siyasa a tsakanin qarshen Turai da qasashen Musulmi. Shi ne kuma ko a jima ko ba daxe zai kai duniya ga tudun tsira!

Mulkin Dimukuraxiyya duk da naqasunsa, shi ne ake kambamawa a yanzu, don shi mulki ne inda mutanen da ake mulki su ke da dammar sa baki ga ayyukan kafa gwamnati, da kuma ayyukan tafiyar da manufar mulkin gwamnatin. A yanzu mulkin Jamhuriya ke tashe a duniya duk da cewa bai dace da wasu qasashe ba kamar Nijeirya ta Arewa. Saboda ya rusa harsashin mulki, wato Sarakuna a Arewa, wanda yake xaya ne daga Sharrorin Jamhuriya!

Tsarin mulkin Sarakuna bai tafi yadda ake so ba, saboda 'yan Majalisar Wakilai, sai suka riqa yin katsalandan a cikinsa. Wani lokaci kuma har qafar-angulu suke masa don su tauye bunqasarsa saboda wata manufa ta siyasa. Wata qila, tsoron kafuwar mulkin Mulukiya ya sa su aibata wannan tsarin mulki. Takon saqa da Wakilai ke wa mulkin Sarakuna, ya zaizaye qarfin mulkin En'e, wani hali da ya kawo cikas ga ci gaban Arewa. Su 'yan siyasa sai suka jarabtu da son Sarauta da qin Sarakuna da masarautarsu. Wata qila suna son Sarauta ne saboda ganin yadda Sardauna ya zama wani tauraro mai haske a cikinsu da kuma ganin yadda 'yan Majalisarsa suke riqe da muqamin Sarauta. Abin da basu yi la'akari ba shi ne samfurin wancan siyasa ya bambanta da ta sauran lokuta da suka gabata. A wannan lokaci siyasa da Sarakuna ake yi. Kada fa a manta a wannan lokaci 'yan Siyasa na son Arewa ta koma Jamhuriya ne. Saboda haka adawarsu bata wuce ta yaqi da Mulukiya ba.

Duk da haka sai 'yan siyasa su ka riqa yin shisshigi a cikin harkokin Sarakuna, Sardauna, sai ya gargaxe su da su daina! Lokacin da Majalisar Wakilai take cikin kwamitin bayarwa da ta zo kan ajin ofishin ministan Mulkin En'e, sai wasu wakilai ba su goyi bayan shawarwari nan da a ke cewa a naxa Sarkin Hausawa a Jos ba. Saboda a maimakonsa suna so a naxa Magajin Gari. Alhaji Yunusa Maihajja ya ce to,idan ba a son yin Sarkin Hausawa a Jos,sai gwamnati ta karvi mulkin Jos,kamar yadda ta karvi Kaduna. Amma wasu wakilan kuma suna so a

[1] A.M. Sa'adu Zungur, shafi na 356.

naxa Sarkin Hausawa a Jos da Makurxi.[1] Akasarin jama'ar garin Jos na son a naxa masu Sarkin Hausawa amma sai shisshigin da 'yan siyasa ke yi a kan wannan batu ya kawo masu cikas.

Firimiyan Jihar Arewa ya ce ko da ma yana zaton wannan magana za ta taso, yana kuwa shiri kanta.A lissafin yawan Mutanen Jos na qarshe ya nuna mutane dubu talatin da xaya da xari shida da sittin da biyar (31,665) ke zaune. Daga cikinsu akwai Hausawa dubu goma sha-bakwai da xari huxu da hamsin da biyar (17,452). Sauran 'yan Arewa da ke zaune a Jos su dubu huxu da sittin da tara (4,069), Ibo dubu shida da xari bakwai da arba'in da bakwai (6,747), da Yarbawa dubu xaya da xari shida da casa'in da biyu (1,692). Ya ce yana shirin ya tambayi Razdan na Jos ya nemi ra'ayin mutane ko suna son Sarkin Hausawa ko kuwa Magajin Gari.[2]

Sir Ahmadu Bello ya yi jawabi kan dangantakar 'yan Majalisar Wakilai da mulkin En'e. Ya ce, akwai bambanci qwarai tsakanin sha'anunuwan gwamnati da na mulkin En'e.Ya ce idan gwamnati ta ba En'e-En'e iko,suna so ne su tafiyar da sha'aninsu da kansu sosai da kuma sanin ya kamata, don haka sai ya gargaxi Wakilai,cewa su wakilan jama'a ne gaba xaya ba na En'e ba.Ya ce ko kaxan kada 'yan Majalisar Wakilai su riqa shisshigi game da sha'anin mulkin En'e-En'e.Kada su xauki kansu kamar Hakimai ko su qirqira wani ofis don kawo qararraki.Ya faxi hukuncin da za ayi wa wanda ya yi qoqarin vata ikon mulkin En'e-En'e.

Ya ce ba yana ba Wakilai shawara ba ne cewa kada su bar ba Majalisun En'e shawara kan abin da ya shafi gwamnatin jiha. Amma idan za su yi haka xin, sai su tuna da kaifaffan layin da ke tsakaninsu. Kuma ko kusa kada su yi amfani da muqaminsu don su samu wata faida na Jam'iyyarsu ta siyasa. Sardauna ya ce lokacin da suka halarci taron jam'iyyarsu sai Wakilai su fayyace sosai cewa ba suna nan ba don su wakilci En'e-En'e,amma suna wakiltan abin da ya shafe su ne kawai. Wakilai da dama na gwamnati da sashen 'yan hamayya, sun yi jawabin goyon bayan jawabin nan na Firimiya.[3]

A Arewa siyasa da Sarakuna a gwame suke basu rabuwa Alal misali, maganar naxa Sarkin Jos ta sake tasowa a farkon shekarar 1957, Alhaji Audu Gobe-zan-tashi, na jam'iyyar NPC reshen Jos ya bayyana buqatar reshen wannan qungiya a taronta da tayi inda ta bayyana yadda shirin Sarautar Hausawa ya kafu tun lokacin da aka kafa garin Jos.

---

1 G.T.K 15 ga Maris 1957 shafi na 4.

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*

Ita Jos, an kafa ta cikin shekarar 1914 ne, a lokacin tana qarqashin Bauci. Ana naxo Hakimi daga can, amma duk da haka akwai Sarkin Jos wanda sha'anin garin duk ke hannunsa. Ga lissafin Sarakunan Hausawa tun da aka kafa Jos:

Wanda ya fara yin Sarautar Hausawan Jos, shi ne Garba Namatanyawa shi ne Sarkin Hausawan Jos na farko, daga shi sai Ahmadu Xan Inuwa sauran su ne, Buraima, da Salihu, da Audu Sarkin Ningi, da Garba Xan Tafida, da Garba, da Waziri, da Usman Kura, da Samanja Sa'idu. Daga nan sai Isyaku. Tun daga kan Isyaku ne, ba a sake naxa Sarkin Hausawa ba a Jos, sai Magajin Gari. Jam'iyyar NPC reshen Jos, ta ce zai fi kyau, En'e ta Jos ta duba wannan magana da idon basira, ta naxa Sarki don zai fi amfani.

En'e ta Jos, ta yi kunnen uwar shegu, da wannan kira da aka yi mata ta ce ba za ta yarda ta naxa Sarkin Hausawa a garin Jos ba. Wannan shi ne amsar da En'e ta Jos ta aika wa Alhaji Audu Gobe-zan-tashi, shugaban NPC reshen Jos. Ta qara da cewa a bisa sakin layi na hamsin da shida na Dokar En'e-En'e ta shekarar 1954, da kuma shawara tsakanin shugabannin Jam'iyyoyin Siyasa da Wakilan Qabilun Jos, aka kafa Majalisar Gari da aka zava ta hanyar asiri a cikin shekarar 1954 da za ta riqa lura da sha'anin garin Jos.

A kan haka, Majalisar da taimakon Wakilan gari, wanda yake shi ne mataimakin shugaba su ke da ikon duba sha'anin garin Jos. A takardar amsar En'e ta Jos da ta aikawa reshen wannan Jam'iyya ta qara da cewa ai Majalisar garin Jos ba ta ka sa aikinta da aka aza mata ba ne, Wakilin Sarkin Jos, shi ya sa hannu a wannan takardar.[1]

Garin Jos, ko da yake an kafa shi kamar garin Kaduna, amma ya fi garin Kaduna dacewa da samun Sarki. Saboda ita Kaduna farfajiyar Arewa ce baki xaya. Naxa mata Sarki zai iya kawo sauyi a bisa tsarin darajar Masarautun Arewa. Da garin Jos ya samu Sarkin Hausawa da rikice-rikicen da ke addabar wannan gari a yanzu, da basu taso ba. A dalilin rashin samun haka ne har ake xaukar Hausawa baqi a garin Jos, a garin da suka kafa suka kuma taimaka wajen bunqasa shi. Amma shisshigin da 'yan Siyasa suka yi a harkokin sarauta shi ya kawo tarnaqin hana cimma nasara wajen qarfafa Sarki da masarautarsa a garin Jos. Domin akwai gidan sarautar Hausawa a wannan gari.

Idan aka dawo kan maganar Sarakuna a siyasa sai aga tsarin tafiyarsu ya yi kyau sosai ya kuma tasirantu akan jama'ar Jihar Arewa sosai. A watan Janairu na shekarar 1957 ne shugabancin Majalisar Sarakuna ya koma hannun Sarki.[2] Wannan ya nuna akwai sahalewar waxannan Majalisu.

Majalisar Sarakuna ta Jihar Arewa ta buxe taronta a Xakin Shawara a Kaduna ranar Alhamis. Am buxe taron yadda aka saba.Sarkin Gwandu, M. Haruna, shi ya

---

[1] GTK, 11 ga Janairu, 1957. shafi na 11

[2] *Ibid*., 22 ga Fabrairu, 1957

shugabanci Majalisar kafin Mai girma gwamnan Jihar Arewa ya iso. Wannan shi ne lokaci na farko da wani Sarki ya shugabanci Majalisar. Lokacin da Gwamna ya iso ya karanta jawabinsa da Hausa. Jawabin iri xaya ne da wanda ya yi a Majalisar Wakilai ranar da aka buxe taro.

Gwamna Sir Bryan ya yi murna saboda warkewar Etsu Nupe. Ya ce ya sami saqo daga Sarkin Kano wanda yanzu ke Ingila,yana wa majalisar fatar alheri.Gwamna ya yi magana kan ritayan Razdan na Zariya Mr. C.V. Williams, wanda shi ne muqaddashin Shugaban Majalisar, kuma wanda ke riqe gwamnati in Gwamna ba ya nan.

Gwamna ya yaba da yadda ake tafiyar da mulkin En'e-En'e. Ya ce akwai alamar qwarancewa da inganci.Saboda haka ne yake so ayi qoqarin qusoshin En'e-En'e su riqa zuwa Kwas a Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya. Gwamna ya gode wa Sarakuna da su ka Wakilci Arewa a Majalisar Nijeriya ta da, da kuma cikin kwamiti-kwamiti na gwamnatin Nijeriya. A wannan zamani Sarakuna na cikin sha'anin siyasa ne ka'in da na'in sun kuma bada qasaitacciyar gudunmawa wajen ciyar da Arewa gaba.

A qarshen jawabin Gwamna, ya gargaxi Sarakuna da sauran ma'aikatan En'e da kuma duk masu hannu kan jama'a su riqa hanzari kulli yaumin domin su kasance suna sane da duk abin da duniya ke ciki. Saboda haka zuwa Kwas a Makarantar Koyon Mulki zai qarawa Sarakuna ilimin mulki da fahimtar zamani. A wannan zama ne sai Shehun Dikwa ya kawo shawara cewa Majalisa ta roqi Gwamna ya isar da saqon godiyarta ga Mai martaba Sarauniyar Ingila saboda xawainiyar da ta xauka na ziyararta zuwa Qasar nan irin dai wanda aka tabbatar a Majalisar Wakilai. Shehun har wa yau ya kawo wata shawara cewar yana so a sanya wani abu a Xakin Shawara na *Lugard Hall* domin tunawa da Sarauniya. Sarkin Fika Muhammadu shi ne ya goyi bayan shawarwari.[1]

Ko da yake Wakilai sun yi na'am da wannan kira da Firimiya ya yi masu a zahiri na kada su riqa shisshigi a mulkin En'e, amma dangartakar Majalisar Wakilai da ta Sarakuna ba ta sake zane ba. Ana kusanto wa ga samun 'yanci, sai qarfin Majalisar Sarakuna na zaizaye wa, na Majalisar Wakilai na qara qarfi. Duk da haka, gwamnan Arewa ya tafiyar da mulkin waxannan Majalisu cikin lumana.

Sir Ahmadu Bello, ya yi qoqarin ganin ya kawo sahalewa tsakanin 'yan siyasa da Sarakuna, amma qoqarinsa sai ya ci tura. Saboda adawar 'yan Siyasa da Sarakunansu sai ta xauki wani sabon salo, mulkin Sarakuna kuma ya ci gaba da zaizayewa. A sabili da haka ne sai majalisar Wakilai na qara qarfi ta Sarakuna kuma na raguwa. Dalili kuwa 'yan siyasa na hangen qarshen mulki ta kan Sarakuna na qaratowa, suna kuma son Arewa kamar Kudu ta koma Jahuriya. Duk da haka waxannan majalisu suna tafiya tare, suna kuma tattauna abubuwan ci

[1] GTK, 27 ga Maris 1956 shafi na 2

gaban Arewa, a tarukan su. Amma daga shekarar 1957 ne dangartakar da ke tsakaninsu ta shiga tavarvArewa sosai. Daga wannan shekara ce har ya zuwa shekarar 1960 dangartakar waxannan majalisu ta fara xauqar wani sabon salo.

Kuma tun da yake tsare-tsaren mulki da a kan yi bisa ra'ayin jama'ar qasa a kan yi su, a kan sauya waxannan tsare-tsare kowane lokaci don ya dace da buqatun zamani. Mulkin Dimukuraxiyya na ainihi, shi ne irin mulkin da mutanen qasa suka yarda da shi sosai, kuma su ke goyon bayansa. Hanyar mulki da Majalisa na Ingila yana xaya daga cikin hanyoyin mulkin Dimokuraxiyya na ainihin waxanda aka fara kafawa duniya. A zamanin Siyasar farko a Arewa, Majalisar Sarakuna ta fuskanci wasu matsaloli.

Matsalolin Majalisar Sarakuna

Sardauna ya juyo kan matsalolin Majalisar Sarakuna, inda ya ce:

"Sai kuma mu dubi irin Mulkin En'en da zan yi tu'amuli da shi. Kada fa ka zaci En'e-En'e tun da ma can haka su ke kamar yadda su ke a yanzu. Sun ci gaba qwarai, kamar yadda komai ma ya ci gaba, tun daga lokacin da su ke 'yam mitsi-mitsi har suka qasaita yadda su ke yanzu, ba su kuwa daina qara qasaitar ba. Akwai sauran ci gaba iri-iri, da za su kai gare su nan gaba. Amma bari mu duba mu ga a kan wane harsashin za a yi ginin. Irin mulkin Gwamna Lugga na can farko, shi ne na Sarki da Majalisa, waxansu cikin 'yan Majalisar na gargajiya ne, waxansu kuma waxanda ake so ne, shi ya sa aka sa su ciki, sai kuma magatakardu masu rubuta abin da aka shawarta. Su 'yan Majalisar nan ba sa jin suna xauke da nauyin alhakkin kowa im ba na Sarkin ba, wanda ya naxa su ya kuma tsaida muqamansu. Kullum suna nan a hedkwatar da Sarkin yake, ba safai za su je wani wuri ba. Sarkin ya kan yi shawar da su kafin ya zatar da kowane al'amari, galiban kuwa ya kan yi aiki da shawarwari da suka bashi. Galiban wurare duk suna da Hakimai, waxansu daga cikinsu suna da abin da a wannan zamanin za mu iya kira qasashen Hakimai, waxansu kuwa gonaki kurum gare su a can daji, ko da yake dai gonakin masu girma ne. sun dai fi so su zauna a hedkwata, domin idan su je qauye me yiwuwa ne a manta da su. Don haka kullum sai munafince-munafince da qulle-qulle iri-iri ko a halin yanzu ma ban ce za a rasa yin haka ba.

Sai kuma Dagatai. Su ne ke kula da zaman lafiya na jama'a baki xaya. Su ne su ke kamo masu laifi, su kuma ga ana kiyaye Odoji da dokoki cikin yankin wuraren da ke qarqashinsu. A dalilin haka ne ma yasa ba su cika samun wani taimako daga waje ba, ko gobe kuwa haka sha'anin yake. Su ne ke taro harajin nan iri-iri, ta hanya mai wuya, waxanda daga baya ne aka cure su, suka zama haraji iri xaya tak da kuma jangali. Ban san yadda suke yin irin nasu lissafin wajen tarawar ba, amma dai basu tava yin kuskure yadda mai biyan zamana ya

qware su ba. Domin idan sun tara za su kai wa shugabanninsu ne, bayan sun xebi nasu rabon qanqane."[1]

A qoqarin 'yan siyasa na cimma nasarar zaizaye ikon Sarakuna da tasirinsu akan jama'a, sun duqufa baji-ba-gani wajen muzanta Sarakuna da zarginsu da tafka rashawa da cin hanci a cikin mulkinsu. Dalilin yin haka shi ne domin qwancin da suke wa Sarakuna wai sun kakkame komai da komai a qarqashin mulkinsu. Saboda sai ana haka Arewa zata karkata ga mulkin Jamhuriya. Sardauna bai ga akwai hujjar yin hakan ba. Saboda sai ya kare Sarakuna ne da bayanai masu gamsarwa

Zargin Cin Rashawa

Abokan adawar Sarakuna suna zargin mulkin En'e da cin rashawa, da almubazzaranci da murxiya tare da danniya. Sun xauki kamfe na vatanci ba don komai ba sai don su aibantasu su kuma zai-zaye qarfin mulkin Sarakuna don su samu wanzuwa. A lokuta da dama akan kururuta laifin Sarki, Hakimi ko Dagaci ba don a hukunta mai laifi ba, a'a, sai don a vata masarautar baki xaya, don a qara ma ta muni a idon jama'a. 'Yan Siyasar Jumhuriyar farko waxanda suka xauko yaqin qwatar 'yanci, sun yi amfani da duk wata hanya da za ta basu damar karya qarfin mulkin Sarakuna, a hankali kuma cikin hikima ba tare da tashin hankali ba, sun cimma nasara.

Sardauna a matsayinsa na Basarake kuma qasaitaccen xan siyasa, ya yi qoqarin kare irin wannan qazafi da zargi marasa tushe da a yawancin lokaci ake wa Sarakuna. Firimiya ya ce:

> *Maganar Majalisun En'e En'e xin nan ba ta cika ba da wahala ba qwarai. Amma cin rashawa babbar magana ce, wadda take sa mu dogon tunani. To, a nan ina fata masu karatu za su yafe mini don in bar bayanin da nake yi da, in shiga wani abu mai sauqi a ce a daina cin rashawa, sai ka ce ita rashawar fitilar lantarki ce, wadda in ka valla mavallinta sai ta kama, ko ta mutu, ko kuma kamar bakin famfo. Ita rashawa aba cewadda ta samo tushe tun daga farawar duniya. Akwai wata qasa a duniya wadda za ta fito tsakani da Allah ta ce ita sam-sam mutanenta ba su cin rashawa? Ba na zaton haka. Waxansu kam ba shakka sun fi waxansu, amma muddin dai maza da mata na duniya suna nan yadda suke, ba za a rasa waxansu daga cikinsu da za su qi yin aiki don jama'a ba, sai dai domin kansu. Irin su ne ke matsa*

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na .110-111.

lamba don ayi wani abu, su sami riba. Irinsu ne kuma ke da dukiya ko muqami waxanda za su yi amfani da su, don su yi saurin samun wani abu na ribace ribace da sauran samun abubuwa, ba lallai su kasance kuxi ne kurum ba. Mai yiwuwa ne su zama bayyanannun abubuwa ko voyayyu, amma dai duk xaya ne, ta dai mugunyar hanya dai aka same su.

Ni a ganina, iyakacin abin da gwamnati za ya iya yi kan wannan hali shi ne ta murtuke fuskarta, ta harari sha'anin, ta yi qoqarin ganin ba a wuce minsherin al'amarin ba. Mu kan kevancewaxansu Turawa kaxan game da yadda 'yan uwansu su ke xaukar Baqin Mutum da gwamnatin Baqin Mutum duk kowane al'amari na Baqin Mutum cewa akwai vatanci na cin rashawa a al'amarinsu kowane iri. Wannan ba wai rashin kyautawa bane, kuma maras tushe, amma ya nuna mana a fili yadda ta haka a ke gangarawa ga wulaqanta Baqin Mutum, ba don komai ba sai don yana Baqin Mutum xin kurum. To, shin su Turawan mene ne? Gwargwadon yadda na sani dai, ba su da wani mizani na gaskiya, ko tsarin qwaqulo rashin gaskiya. Su ma fa sun bambanta, ba wai tsakanin irin wannan da ke kan waxansu muqamai da waxancan ba su da shi ba, ko tsakanin wannan mutum ma da wancan da suke dai-dai wa daida. Ba duk Turawa ne suka je makarantun nan na 'ya'yan masu sukuni ba, wato Eton da Harrow da Winchester ko waxanda suka je can xin ma, waxansu cikin su kan ba da kunya. Akwai kuwa bambancin mizani iri-iri a tsakanin hawa hawa na daraja ta kowane taron jama'a, a qasashe daban-daban. Haka kurum a tsani Baqin Mutum a ce bai dace ba ko kaxan, kamar yaadda za a girmama kowane Farar Fata, ko na kirki ko lalatacce ne. A shirye dai muke, gwargwadon yadda muke iyawa, ba za mu bari wani ya samu riba ba ta hanyar cin rashawa. Kuma ba za mu bari cin rashawa yaci mu, yaci mu, har ya zame mana jiki ba."[1]

Sarakuna basu xauki maganar cin rashawa da wasa ba. Domin sun xauki yaqin kawar da wannan mugun hali a Arewa baki xaya. A dalilin haka ne ma su ne farko wajen yaqi da karvar rashawa da cin hanci a tarihin Arewa. Yaqin da suka xauka domin ya tsarkake mulkinsu da kuma mulkin qasa baki xaya. Sarakuna da yawa sun tsarkake kansu kafin su kai wannan yaqi ga jamarsa. A dalilin haka ne Sarkin Musulmi Sir Abubakar ya yi kiran jama'ar Arewa da su taimaka wajen yaqin wannan mummunar al'ada. Duk da cewar mulkin Dimukuraxiyya bai

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na . 218 & 219

yiwuwa sai da rashawa, Sarakuna sun yi namijin qoqari wajen rage wannan annobar da ta kunno kai a Arewa

Yaqi da Rashawa

Al'amarin rashawa da cin hanci ya daxe yana ciwa qasar nan tuwo a qwarya. A Arewa saboda hamayyar da ke tsakanin majalisun nan guda biyu, wato Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai sai aka riqa samun yawan qazafin cin rashawa da al'mubazzaranci a kan Sarakuna. Amma kuma qazafi ne maras tushe saboda a akasarin lokuta ana yi ne saboda biyan buqatar siyasa don ana yi ne a baqanta Sarakuna, a raba su da jama'a. 'Yan Siyasa sun lura in ba su rusa tsarin mulkin En'e ba, to, ba za su sami dama da galabar kafa muxlaqin mulkinsu a Arewa ba.

Duk da haka a tarihin Arewa, Sarakuna ne suka fara fitowa fili suna yaqar wannan bala'i don a yi maganinsa ba a Arewa ba ma har ma a duk faxin Nijeriya baki xaya. Sarakuna sun daxe suna gargaxin Hakimai, da Dagatai da masu Unguwanni da su tashi haiqan wajen faxa da cin hanci da rashawa, su riqa kuma yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a. Saboda zargin da 'yan siyasa ke yi, na vatanci ne kawai a farkon shekarar 1954 ba na neman gyara ko hukunta duk wanda aka kama da laifin aikata wannan baqar al'ada ba ne.

Alal misali, waxansu ma'aikatan En'e-En'e da aka same su da laifuffuka iri-iri su sata, da su yin bocar iska da sauransu. An gurfanar da mutane takwas a gaban shari'a. Wannan sharia ta gamo har da wani xan Majalisar Nijeriya, wanda aka jefa shi kurkuku wata shida. Mutum takwas da aka samu da laifi, an xaure su bayan an sallame su daga aikin En'e. Dam majalisar Nijeriya wanda kuma xan majalisar Sarkin Katagum ne ba a tsahirta masa ba. Kantoma mai daraja ta xaya ya yanke shari'arsa a Jos. Ya ce sai ya je kurkuku ya yi wata shida tare da aiki mai tsanani saboda laifin da ya aikata.[1] A wannan yaqi da zalunci a lardin Bauci, sai aka xaure waxannan manyan En'e guda takwas. Haka kuma xan majalisar Sarki kuwa sai ya sami xauri mai tsanani. Akwai irin waxannan misalai masu yawa a sassan Arewa.

Sarakuna sun xauki wannan yaqin bil-haqqi da gaskiya. Saboda sun fahimci Arewa na buqatar ci gaba ta riqa kuma tafiya sau da qafa da zamani. A wannan zamani da ke tafiya cikin hanzari, cin hanci da rashawa ka iya maida Arewa fifa-iya-koma-baya.

A dalilin da yaqi da rashawa da Sarakuna suka xauka ne ya fito fili aka bayyana wa jama'a cewar kixa ya sauya tilas kuma rawa ta sauya, a watan Agustan shekarar 1951, Haxaxxiyar kwamiti ta Jihar Arewa ta ce a yi binciken

[1] GTK Ta 595, 3/2/1954

sha'anin kyautar al'ada ga Sarakuna, Hakimai da Dagatai da jama'a.[1] Tun da an xauka kyautar al'ada ga Sarakuna, wani nau'i ne na rashawa. Saboda haka Majalisar Sarakuna ta soke irin wannan kyauta mai kamar toshiyar baki. Ko da yake an san akasarin kyautar al'ada bata da alaqa da rashawa ko cin hanci. Amma duk da haka sai Sarakuna suka soke ta.

Kyautar al'ada ta tsokale wa 'Yan Siyasa ido domin haka ne suke neman hanyar da za su yi wa wannan al'adar karan tsaye! Wataqila an xauka ta wannan kyautar ne Sarakuna ke qara bunqasa arziqinsu saboda haka sai 'yan adawa suka jingina irin wannan kyauta da rashawa. Sir Bryan Sharwood Smith ya bambance tsakanin rashawa da cin hanci, inda ya ce: "To, da al'ada da Musulunci duk ba su hana Sarki ya amshi hasafa ba daga jama'arsa. Domin kuwa in ba da xan abin da ke shigowan nan ba, albashin ba ya iya xaukar wannan ximbin kaya. Hasafi fa na ce ban ce rashawa ba. Rashawa shi ne sha gari xauki garma, hasafi kuwa shi ne kyautar al'ada."[2] A cikin watan Fabrairun shekarar 1952, sai Sarkin Gwandu Sir Yahaya ya bada shawarwari a buxe muhimmin yaqi da rashawa. Sarakuna suka yarda. Don dai a fahinci komai da komai a fili sai gwamnatin jiha ta sa aka yi rahoton kyautar al'ada. An kuma fayyace komai dalla-dalla, an kuma bambanta kyauta da rashawa. Saboda an daxe ana jingina irin wannan kyautar al'ada da rashawa don a vata Sarakuna da masarautunsu. A sharhin Editan Jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo, ta watan Maris na shekarar 1954 ya ce:

"Mu kam muna ganin duk wani goce-goce ne kurum. Kowa ya sani, im babu mai bada rashawa, haqiqa ba za a sami mai karvarta ba. Haka kuma im babu mai karvar rashawa, ba za a sami mai ba da ita ba. Don haka a cikin shari'ar musulunci, da wanda ya ba da rashawa da wanda ya karveta, dukkansu biyu suna da laifi. Na biyu, ba mu ga hujjar da za ta sa a riqa kewaye-kewaye ba. Domin misali, marigayi Sarkin Gwandu Sir Yahaya, da ya yi niyyar yaqi da rashawa, ya ci nasara kanta. Shi ba ya karva, wanda kuma ya karva, da ma zai yi masa horo irin wanda ya cancanta. Ta haka ya hana masu son bayarwa bayarwa.

"Ashe in magabata duka da yake an fi jin magana tasu, suka fito fili suka ki karvarta, suka qi sassauta wa wanda ya karva da wanda ya bayar, sauran jama'a kamar kowa ya dage, ba zai bayar ba, ba kuwa zai karva ba, cikin xan lokaci qanqane, yaqi da rashawa zai qare."[3]

Sarakunan Arewa sun xauki yaqi da rashawa bilhaqqi da gaskiya jama'a kuma sun daxe suna yabon Sarkin Gwandu Sir Yahaya wanda ake wa laqabi da "Mai Gaskiya" saboda shi ne mutum na farko da ya fito kai tsaye wajen yaqi da

---

1 Sharhin Edita, GTK 24/3/1954

2 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 23.

3 *Ibid.*,

wannan mummunar al'ada, jama'ar Arewa da yawa sun goyi bayansa, har kira suke da a kwaikwayi halin Sarkin Gwandu Sir Yahaya. A irin wannan kiran ne wani mai suna Malam H.A. Aminu daga Gwambe ya rubuto wa Edita wannan wasiqa:

> *Zuwa Ga Editor – Bayan gaisuwa, na sha karantawa a Gaskiya, irin labaran da ku ke bayarwa game da marigayi, Sarkin Gwandu Sir Yahaya. Ina godiya bisa dukan bayanin da aka bayar game da shi. Sai dai kuma ina roqo ka isam mana da roqommu ga shugabanin mulki, daga Ministoci har zuwa kan Dagatai da masu unguwanni, su kwaikwayi halin nan na Sarkin Gwandu Sir Yahaya da irin adalcinsa. Na tabbata idan suka yi qoqarin xaukar halin nan nasa, lallai zai taimake mu qwarai ga taimakon kammu, mu kuma iya riqe kammu da kammu.*[1]

Editor ya amsa:

> *Idan ka lura, Gaskiya tana yawan maimaita wa shugabanni da sauran jama'a kyakkyawan mulkin da marigayi Sir Yahaya ya yi. Dubi jerimmu ma a Gaskiya ta 602, ka gani. Dalilin yawan ambaton wannan bawan Allah, shi ne don mu ja hankalin shugabanni, su kwaikwayi wannan adali, domin in suna yin koyi da shi, babu shakka cin hanci da rashawa, tare da dukkan cuce-cucen da su ke kawowa, za su tattara kayansu su bar Arewa, yadda suka bar qasar Gwandu.*[2]

Sarkin Gwandu Sir Yahaya, a muwayacin lokaci a Arewa ne ya fito fili ya nuna yadda za a cin nasara akan yaqi da cin hanci da rashawa, ta furuci da aiki. A lokacinsa, sai ya zama Sarki qi-faxi a gwagwarmayar yaqi da rashawa da cin hanci. Gwamna Sir Bryan ya yabi wannan Sarki wanda ya hau gadon sarauta bayan rasuwar xan'uwansa Sarkin Gwandu Usuman, ga abin da ya ce: "Da shike shi Yahaya ya sha inuwar *Katsina Training College*, sai ya zama xaya daga cikin jagororin ci gaban Arewa. Sarkin Gwandu Yahaya, Alqur'ani don gaskiya ake tsoronka! (kirarin na mai fassara ne)."[3] Wannan kirari ne da ya dace da shi qwarai da gaske.

Akwai irinsa da yawa a wannan qasa, wato Sarakunan da suka yi suna wajen tuwalu'u da adalci, waxanda kuma shugabancinsu ne ya ciyar da Arewa da

---

1 GTK, 31/3/1954, shafi na 2

2 *Ibid*.,

3 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 23.

jama'arta gaba. Har ila yau Allah Ya azurta Arewa da Sarakuna masu gaskiya da riqon amana waxanda ke tafiya tare da zamani har gobe.

Mulkin Sarakuna ya fi shekara dubu a Arewa, ya kuma yi kyakkyawan tasirantuwa akan jama'arta. Kowa ya sani, Hausawa su kan ce, "Ba a yin dabo sai da riga." Haka kuwa ba a yin sarauta sai da jama'a. Amma ba za a ji daxin sarautar ba, sai da tsayawa bisa hanyar adalci da shafewa jama'ar da ake mulki hawaye. Domin kuwa Sarki na jama'a ne, jama'a kuma na Sarki ne. Amma idan aka kasa dai-daitawa da juna, zaman zai yi wuya. Sarakuna sun fahimci zamani da irin illolin da rashawa da cin hanci za su haddasa wa jama'arsu. Don za su kawo rashin daidaituwarsu da jama'arsu. A dalilin haka suka tashi haiqan wajen yaqi da rashawa da cin hanci. Sarkin Musulmi Sir Abubakar Sadiq sai ya fito ya kira 'yan Arewa da babbar murya da su himmatu wajen cimma nasara a wannan yaqin jihadi da cin hanci da rashawa.

Shelar Sir Abubakar

A wannan rikirkitaccen zamani na Siyasa Sarakuna sun fahimci jama'a suna son komai za a qulla, a qulla shi da yardarsu. Komai za a kwance, a kwance shi da yardarsu. Saboda haka a yaqi da rashawa da cin hanci, sai aka nemi yardarsu da haxin kansu don a cimma manufa. A dalilin haka ne kuma Sir Abubakar ya yi bayani, a shelar da ya yi wa jama'ar Arewa, inda ya ce: "Mun tabbatar, ni da Majalisata, za mu yi tsaye, da taimakon Ubangiji, mu ga adalci ya gudana cikin qasar nan. Kowane, wanda ya karkata zuwa ga tafarkin zalunci, ko na rashin gaskiya, bayan shelar nan tamu, za mu ga ya samu horo mai tsanani wanda ya cancanta, ko shi wane ne."

Wannan yana daga cikin abubuwan da Mai girma, Sir Abubakar, ya ce a cikin shelar da ya sa aka yi a rubuce, zuwa ga dukkan jama'ar da ke cikin mulkin qasar Sakkwato da Arewa baki xaya. A wannan shelar ce Mai martaba ya yi wa jama'arsa a rubuce, inda ya ce:

> *Zuwa ga dukan jama'a na mulkin Sakkwato. Gaisuwa mai yawa da aminci da yarda zuwa gare ku. Bayan haka, dukanku dai ba ku rasa jin maganganu da shawarce-shawarce da ake ciki tun daga bara har zuwa bana, munanan al'adunmu na amshe-amshe na tsakanin magabata da ma'aikata da talakawa. An ga dai ba bin da ya vata Nijeriya dukanta kamar waxannan al'adu. Sun dami qasar nan, sun hana komai ya miqe sosai, sun tauye ci gaban qasar nan. Don shi zama cikin sanin kowa, an yi shawarwari kan wannan al'amari na amshe-amshe da ake yi ta hanyar gaisuwa da kuma wasu hanyoyi na kyauce-kyauce, an kuwa tsai da shawara bisa ga lallai im ba irin*

waxannan al'adu suka mutu ba, ba yadda za a yi qasar nan ta ci gaba sosai, ta sami arziqi da wadata da kwanciyar rai. Sabo da haka mun yi umurni da a yi rubuce-rubuce, don kowa da kowa shi sani, ni da majalisata, mun goyu sosai bayan waxannan shawarwari na kasha waxannan kyauce-kyauce.

Lokacin da muka ce kyauce-kyauce ba muna nufin abin da wani mutum zai ba wani mahukunci ba don shi samu kuvuta daga wani abu ba, ko ko don shi samu wata kuvuta. Irin wannan kyauta kowa ya santa, ita a ke kira rashawa. An ko sani akwai horo ajiyayye na shari'a ga wanda ya yi laifi na karvar rashawa ko bada ita. Kyauce-kyauce da muna Magana, su ne irin su gaisuwa daga ma'aikaci ko talaka zuwa ga basarake, ko daga hakimi ko talaka zuwa ga hakimi, ko wani ma'aikaci, ko daga ma'aikaci zuwa ga na gabansa.

Goro, rago, zabbi, ko kaji na sabka. Ragon layya, zuma ko wani abu na azumi, ko wace irin kyauta ta muna-ga Allah-muna-gare-ka. Doki, rago, kuxi,[1] *majalisata, mun xauka ga kammu za mu hana kammu ga waxannan kyauce-kyauce. Na yi horo ga kowa da kowa, wanda shina cikin mulkin nan, mai iko da talaka, shi yi tsaye shi hana kansa ga waxannan kyauce-kyauce. Kada shi bai, kada a ba shi shi karva. Wanda ya bayas da wanda ya karva, duka biyu sun yi laifi, in an sansu ko wannensu zai samu horo matsananci, wanda ya cancanta. Babu sani babu sabo. Don shi zama cikin sanin kowa, wannan doka za ta kama aiki daga ran 1 ga watan Agusta, 1954. duka laifi wanda aka yi game da dokan nan daga ran 1 ga wata Satumba, 1954, zuwa, irin horon da an yi alqwari cikin n nan.*

Cin Rashawa da Hanci

Ban da wannan kuma muna sake tuna muku, muna nanata muku dukanku, babba da yaro, mace da namiji, mai iko da talaka na cikin mulkin nan, dukanku, ku tashi tsaye ku hana kanku daga karvar rashawa da basheta. Ku hana kanku han'inci game da cin amanoni na harakokinku da aka ba ku. Ko da ma kun sani su karvar rashawa su ha'incin nan a kan kai su. mu tabbatar, ni da majalisata, za mu yi tsaye, da taimakon Ubangiji, mu ga adalci ko na rashin gaskiya bayan n nan tamu, za mu gaya samu horo mai tsanani, wanda ya cancantar, ko shi wane ne.[2]

---

1 GTK, Ta 620, 16 ga Yuli, 1954 shafi na 2

2 *Ibid*., shafi na 5

Tarihi ya nuuna a fili Sarakuna ba su dulmuya cikin rashawa da cin hanci ba don kuwa ko kaxan ba su xaure wa zalunci gindi ba. Sun kuma yi iya qoqarinsu wajen tsarkake zukatansu da zukatan jama'arsu daga muguwar al'adar cin hanci da rashawa. Bugu da qari a tarihin Arewa Sarakuna ne suka fara xaukar jihadin yaqi da wannan mummunar xabi'a. Amma akwai sauran rina a kaba, 'Yan Siyasa na nan tafe da irin nasu salon cin hanci da rashawa. Muguwar al'adar cin hanci da rashawa da Sarakuna ke gwagwarmayar tuge kwayarsa a zukatan 'yan Arewa ya samu karvuwa a Nijeriya. Saboda an fahimci yadda wutar rashawa ke ci a kowane sashen jama'a da kuma illolin da za su haddasa ga wannan qasa. A dalilin haka sai aka nemi a kafa kwamiti na musamman da zai duba cin hanci da rashawa.

Kwamitin Duba Cin Hanci Da Rashawa

A taron Majalisar Nijeriya, Mr. B.C Okwu, xan jam'iyyar N.C.N.C., ya kawo shawarwari cewa, majalisa ta roki gwamnati su naxa kwamitin da za su duba yadda za a bincika cin hanci da rashawa tsakanin ma'aikatan Nijeriya. Wannan batu ya jawo hankalin Wakilai kan cewa cin hanci da rashawa, shi ne ya kawo tawayen qasar Faransi da kuvucewar sarautar Masar ga Sarki Faruku, da kuma abin da ya faru a Golkwas. Wannan mummunan abu yana cikin ma'aikatan Nijeriya, ya kuma shafi sauran mutane. Mr. Okwu ya ce akwai abin da ya faru inda malaman makaranta suka bari 'yam makaranta suka ga takardun jarabawa, don sun ba da hanci. Ba da daxewa ba wannan abu ya faru a jami'a ta Ibadan. Ya ce hatta ma yanzu mutum ba zai sami aiki ba, im bai ba da hanci ba. Malam Hasan Makaman Abuja ya goyi bayansa.

A Arewa 'yan Siyasa sun duqufa wajen mummunar adawa da Sarakuna har suna baqanta su za zargin murxiya da cin hanci. A halin gaskiya kuwa cin hanci da rashawa ya kusa mamaye jama'ar qasa baki xaya. Alhaji Abubakar Imam Zariya ya yi magana kan wannan shawara. Ya gaya wa Majalisa cewa wannan yana cikin abubuwan manufar jam'iyyar N.P.C., su yi yaqi da cin hanci da rashawa. Alhjai Imam ya bada misalai na hanyoyin da suke gaba da cin hanci da rashawa kamar Addinin Buda, da mulkin Rasha da Arnanci, hasalima dai ya ce duk kalmomin da suka qare da *isms* suna gaba da cin hanci da rashawa. Daga nan sai ya gaya wa Majalisa cewa Jihar Arewa ko da ma ta fara yaqi da waxannan muggan xabi'u. Alhaji Imam ya ce in da ace ya zama gwamnan Nijeriya, zai fuskanci yaqi da waxannan mugwayen abubuwa.[1]

A lokacin da Majalisa take taronta a Ikko an zartar da wani batu da wani xan NCNC, Mr. B.C. Okwu, ya kawo cewa, gwamnati ta naxa kwamiti don su binciko hanyoyin da ake bi wajen cin hanci, da kuma hanyoyin da za a bi domin toshesu. A nan ne Alhaji Abubakar Imam ya qara bayyana wa Majalisa cewa, kashe cin

[1] GTK Ta 602, 24/3/1954

hanci yana cikin babban burin Jam'iyyar da yake ciki, wato N.P.C. Alhaji Imam ya ce, a ganinsa abin da ake nufi da cin hanci shi ne kowace irin kyauta, muddin dai an yi ta da niyyar sha gari xauki garma. Alhaji Abubakar Imam ya zana abubuwa huxu da zai yi, da za a ce shi ne gwamnan Nijeriya, ya ce: "Bayan na sanya duk jihohi sun ci gaba, sun zama kamar Jihar Arewa, na farko sai in sa duk a yi shela wanda duk yake da qarar wani kan cin hanci to, ya kawo masa kafin rana kaza.

"Mutumin da duk aka samu da laifi na farko, sai a yi masa gargaxi mai tsanani. Su kuma waxanda suka kawo qarar a tsare su daga sharrin da za a so a yi musu a gaba. Wannan muhimmi ne, domin sai a haka ne waxanda suka tava yin irin wannan laifi za su ji daxin kawo qara in sun ga wani ya yi. Kuma ba za a sami damar yi wa wani maqarqashiya ba. Ta haka sai kowa ya zama soja na wajen yaqi da cin hanci.

"Na biyu, bayan lokacin nan ya cika sai kuma in sa a yi shela a ko'ina cewa, wanda duk aka samu da laifin cin hanci, to ya kuka da kansa. Na uku, sai kuma in sanar da kowa cewa zan sanya 'yan Sandan ciki ko'ina da don su taya ni farautar wannan mugun abu.

"Aikina na huxu shi ne, in sanar da Sarakuna a fili cewa, akwai babban bambanci qwarai tsakanin ayyukansu da na alqalai. Alqali an naxa shi musamman don ya zauna kotunsa ya yi shari'a da ta zo gabansa. Ba aikinsa ba ne ya je ko ya aika farautar masu laifi.

"Sarki kuwa aikinsa ba ya zama kawai ya jira sai abin da aka kawo gabansa. In ya yi haka, to, bai zama Sarki ba ke nan, ya zama alqali na biyu. Aikin Sarki ne ya aika da mutane qwararru, su bincika inda duk laifi yake su kawo gaban shari'a. In ba haka ba kuwa, to, Sarki bai yi aikinsa ba ke nan. Aikin Sarki ne ya buxe kunnuwansa, ya saurari ko wane mutum da ya kawo masa rahoton cin hanci ko rashawa, ko da kuwa shi wanda ya kawo rahoton cin hancin ba ya cikin masu laifin. In ba haka ba Sarki bai yi aikinsa ba ke nan. Wahalar da duk mai xan qarfi ya sha a hannun mai qarfi, to, zargin yana kan Sarki ne, shi ne bai yi aikinsa ba."[1]

Alhaji Imam ya qarasa da cewa, irin duk abin da ya faxa a nan sama ba shi ne ya qago shi ba, a'a, wannan yana akwai shi a cikin shahararriyar waqar nan da Shehu Magili ya rubuta wa Sarkin Kano, yau fiye da shekaru xari da suka wuce, don ta zama Jagorarsa. Za a kuma iya samunsa a cikin sanannen littafin nan da Sarkin Musulmi na farko, Muhammadu Bello, ya rubuta. Ana kiran littafin *Laya'ul Hukkam*, wato Jagoran Sarakuna.[2]

Sarkin Gwandu, Sir Yahaya ne ya fara kira da a xauki yaqi da cin hanci da rashawa. Shi ne ya farkar da 'yan Nijeriya a kan amfanin wannan yaqi da

---

[1] GTK, 7/4/1954, shafi na 9.

[2] *Ibid.*

wajibcinsa saboda shi ne ya haifar da batun da Mr. B.C. Okwu ya gabatar a Majalisar Nijeriya a 1954. Wannan shawarar ta Sir Yahaya Mai gaskiya ta samu karvuwa ga Majalisar Zartarwa wadda kuma ta shawarci Sir Bryan Leftana Gwamna da a soma yaqi da wannan cuta. Saboda himmar wannan Gwamna da qarfin ransa sai ga shi ba da jimawa ba har sojan cin hanci sun fara ja da baya a jihar Arewa. Amma idan ana maganar cin hanci sai Sarakuna ake dubawa da tabarau mai qara girman abu wato *Magnifying Glass* ba don komai ba kuwa sai don a sami hanyar da za a bi a rusa muxlaqin mulkinsu.

Tun da farko sai Leftana Gwamna ya shaida wa Sarakuna niyyarsa. Ya shawarce su kada su ajiye mutane da yawa fiye da yadda albashinsu ke iya xauka. Daga nan kuma sai aka naxa kwamiti wadda za ta bincika hanyoyi iri-iri na kyautata al'ada, ta ba ta shawarwarin waxanne hanyoyi za a toshe, waxanne za a bari. Ta haka duk irin miyagun hanyoyin nan na cin hanci a kaikaice aka qwaqulo su aka fito da su fili, aka ce a kashe su. A dalilin haka ne kowane mutum aka kama da laifin cin hanci, to, shi kam ya kaxe, babu wani rangwame, sai horo kawai.[1]

Ko da Sir Ysahaya ya fara kaxa gangar yaqi da cin hanci da rashawa a shekarar 1952, ya yi ne bisa gaskiya bisa kuma koyarwar Addinin Musulunci. Amma ko da Gwamna ya karvi wannan yaqi sai ya karkatar da shi, ya maida shi wata dama da zai yi amfani da ita, ya qara fifige wa Tutocin Shehu Mujaddadi fika-fikan tashi. Don haka ne ya harari kyautar al'ada da ake bai wa Sarakuna a wata hanya ta cin hanci da rashawa. Saboda haka ne ya kafa Haxaxxen Kwamiti Kan Kyautata Al'ada. Abin nufi a binciki Sarakuna a kan abubuwan hasafi da talakawa ke ba su. Duk da cewa akasarin irin waxannan kyautuka na al'ada ba nau'in cin hanci da rashawa ba ne. don ba ana yin su ne da niyyar 'sha gari xauki garma' ba. Amma duk da haka Sarakuna sun xauki kabbarar yaqi da cin hanci da rashawa don kuwa tun kafin zuwan Bature sun san muhimmancin wannan yaqi ta koyarwar Sarkin Musulmi Muhammadu Bello da Shehu Magili.

Kwamiti Kan Kyautar Al'ada

Haxaxxen Kwamiti kan kyautar al'ada da aka kafa don ya duba ya kuma binciki hanyoyi iri-iri na kyautar al'ada ya kuma ba da shawara a kan su, ya fara taronsa a watan Yuni na shekarar 1954, a xakin taro na Sakatariya a Kaduna.

Waxanda suka halarci taron su ne Mr. G. Wilson, wanda shi ne ya shugabanci taron, da kuma tsayayyun Sakatarorin Ministan Mulkin En'e da na ilimi. Akwai kuma wakilan babban Baturen Yaqi da Jahilci, da Baturen Qulla Zumunci da Baturen Wayar Iska. A wannan taro an shawarta Ma'aikatar Qulla Zumunci ta Jiha su yi aiki tare da Kwamitin Yaqi da Jahilci wajen yin hotunan Sinima.

[1] GTK, 31/3/1954, shafi na 9.

Ma'aikatar qulla zumunci ta buga wani abu musamman kan waxansu da suka gamo da cin rashawa da zalunci tare da Kwamitin Gyara Hali. Kwamitin ya shawarta a sami jin labari sosai daga manyan garuruwan larduna.

A roqi Ministan Mulkin En'e da Kyautata Zaman Jama'a ya ba En'e shawara ta hanyoyi da dama na yadda za a yi furofagandar ra'ayin gwamnati kan kyautar al'ada, sa'an nan kuma lallai ne su zama cikin abubuwan da za a shawarta na Majalisun Waje. A kafa wuraren sanarwa a wuraren da mutane ke taruwa.

Kayayyakin kasuwa kuma za a yi amfani da su, kamar buga maganar a kan fakitin sigari da na ashana da sauran su. Masu kula da sha'anin ciniki na Kano da masu kula da aikin kuza a Jos, tare da ma'aikatar yaqi da jahilci, a roqe su kan wannan. Malamai su riqa yi wa 'yan makaranta jawabi da kuma manyan mutane. Duk kowace hanya ta yaxa labari a yi ta don a nuna cewa mai bayar da hanci da mai karva duka suna da laifi.[1]

A wancan zamani mutane ba za su fahimci kafa wannan kwamiti manaqisa ce babba ga Sarakuna ba domin su ake so a tozarta a fakaice. Idan an tabbatar da kyautar al'ada wani nau'i ne na cin hanci, to, Sarakuna masu karvar wannan kyauta su ma suna da laifi ke nan. Saboda haka maqasudin xaukar wannan yaqi shi ne a wofintar da Sarauta a idon jama'a, a kuma maida ita mara amfani. Domin an jivinta cin hanci da rashawa ga Sarakuna kawai ana kuma cunkusa wa jama'a mugun ra'ayi na ba abin da Sarakuna ke yi ban da cin hanci da rashawa da sunan kyautar al'ada. Saboda haka aka tashi haiqan, aka yi amfani da duk wasu hanyoyi na watsa furofaganda don a baqanta wannan al'adar qasar Hausa, sa'an nan a muzanta wa Sarakuna da masarautun Arewa. Wannan babbar illar Mulkin Mallaka ce a kan mulkin En'e wadda kuma 'yan Siyasa suka karva hannu bibbiyu domin cimma buqatunsu na siyasa amma ba na ciyar da Arewa gaba ba.

Duk da an xauki wannan yaqi ne don a talauta a kuma wofintar da Sarakuna amma sai Sarakuna suka fito suka nuna cewa ai ciki da gaskiya wuqa bata huda shi. Saboda haka sai suka zama kan gaba wajen yaqi da cin hanci da rashawa, da duk wata al'ada da ba ta dace da hankali da shari'a ba. Turawan Mulkin sun fi kowa sanin cewa mulkin Siyasa ya fi na mulki Sarakuna wajen tafka maguxi, da cin hanci da rashawa. Amma saboda akwai shirin darkake mulkin Sarakuna don na 'yan Siyasa ya yi tasiri sai aka tashi haiqan wajen furofagandar vatanci da Sarakuna ta jingina masu cin hanci. A lokacin da cin hanci da rashawa suka zama ruwan dare a Nijeriya.

A Jihar Arewa Sarakuna sun yi dabur wajen yaqi da waxannan mugayen abubuwa, waxanda tun kafin Nijeriya ta samu 'yanci suke neman su yi katutu a zukatan jama'a. Wani babban abin da ke dushe yaqi da cin hanci da rashawa shi ne mulkin Dimokuraxiyya. Saboda yana da dangataka ta qut-da-qut da waxannan

[1] GTK, Ta 618, 14/7/1954.

mugwayen. Abin da qasashe ke qoqarin yi shi ne rage qaifi da illolinsu domin samun ci gaba.

Al'amuran jiha da harqallar 'yan Siyasa da Sarakunansu bai hana ci gaba da tafiyar da al'amuran qasa ba. A wannan lokaci ne ake yin taruka a London domin tattaunawa game da samun 'Yancin Mulkin Kan Jihohi. A managanr taron London Sarakuna ne ma a kan gaba.

Tarukan London

Majalisar Sarakuna da ta wakilai su kan yi tarukansu a lokuta daban-daban inda suke tattauna matsalolin Arewa da Qasa baki xaya. Su kan yi zama na musamman inda suke tattauna Tsarin Mulki da tarukan da aka yi a wannan qasa da kuma Taron London.

Mai girma gwamnan Jihar Arewa, Sir Bryan Sharwood-Smith ya buxe taron Istimat na Majalisar Wakilan Arewa a watan Maris xin shekarar 1957. Kamar yadda aka saba dai sai da ya duba faretin 'yan Sanda a qofar *Lugard Hall*. Daga nan shugaban Majalisar Mr. C.R. Niven da Firimiyan Jihar Arewa suka tarye shi. Gwamna ya yi wa Majalisa dogon jawabi kusan minti talatin yana yi. Bayan Gwamna ya fita, sai shugaban Majalisa, Mr. C.R. Niven ya yi xan jawabi na maraba ga dukkan 'yan Majalisa. Ya bayyana farin cikinsa na zama na ci gaban Nijeriya ne gaba xaya.

Daga nan aka ajiye waxannan dokoki gaban Majalisa: Gyaran Dokar Babbar Kotun Jihar Arewa (1957), da Gyaran Dokar Ranakun Hutu (1957), da Dokar Jama'a (1957), da Gyaran Dokar Kamfanin Raya Qasa (1957), da Dokar Kasafin Kuxi na 1957/58 (1957). Za a kafa wata doka da za ta soke Dokar Kuturta ta da, a 1957, Gyaran Dokar En'e (1957) da Gyaran Dokar Laifuka.

Ministan Ilimi na Jihar Arewa, Alhaji Aliyu Makaman Bida ya zana abin da Majalisa za ta yi a wannan mako, sai aka fara muhawara kan jawabin Gwamna. Za a gyara qa'idar Majalisa, yadda zata ba da dama idan za a yi quri'a sai a ware waxanda suka yarda dabam, waxanda ba su yarda ba kuma dabam. Za a riqa yin haka ne saboda an ga akwai qungiyar masu hamayya sosai. Haka a Ikko, a dai-dai wannan lokaci ne aka yi muhawara kan jawabin Gwamna.

Shi kuwa, Sakataren kuxi na Arewa, Mr. P.H.G. Scott ya yi muhimmin jawabin nan nasa na kasafin kuxaxen da za a kashe daga 1957/58. A wannan zama Majalisa ta samu tambayoyi fiye da xari da talatin daga wakilai, fiye da tamanin daga cikinsu za a ba da amsoshinsu da ka ne. Ba a tava samun tambayoyi masu yawa haka ba. Cikin batutuwan da wakilai za su kawo har da ta Mr. J.S. Olawoyin, mai wakilancin Offa wanda yake son a riqa biyan leburorin Arewa sulai biyar a rana. Wakilai 'yan UMBC sun haxa kansu da NEPU su zama qungiyar masu adawa da gwamnati a Majalisa. Za su yarda da ra'ayin juna a ciki da waje.

Cikin manyan mutane da suka je kallon buxe taron Majalisa har da kwamishinan Jihar Arewa a Ingila, Alhaji Abdulmalik, da Sir Algenon Brown, babban Cifjojin Arewa, da Alhaji Aliyu Turaki, Muqaddashin Shugaban Kamfanin Raya Qasa na Arewa da Alhaji Abubakar Imam, xan Hukumar Xaukar Ma'aikata. Ga kaxan daga cikin jawabin Mai girma Gwamna Bryan:

"Shugaban da Mashawarta: Lokacin da na yi muku jawabi cikin watan Disamba sa'an nan ba a daxe da kafa sabuwar gwamnati ba. Saboda haka a lokacin ban iya faxa muku abubuwan da Ministocina ke da niyyar gamawa cikin sabuwar shekaran nan ba. Amma dai kafin in ambace su, tilas ne in ambaci Taron Shirin Mulki wanda za a yi a London. Da yake a cikin zamanin wannan Majalisa ne Jihar Arewa za ta sami cikakken Mulkin Kai, mutanen da za su wakilci Jihar Arewa a taron nan, kowace irin jam'iyya kuwa suka wakilta, za su tafi London ne tare da tabbatacciyar amana da kiyayewar alhakkin nan da jama'a suka xora musu. Na tabbata cewa mutanen Jihar nan waxanda su ke da yawunsu ne wakilai suka je London ba za su ga kasawar wakilan ba. Bari kuma in juyo ga waxansu al'amura.[1]

Duk irin samfurin mulkin da jama'a ke bi adalci shi ne man fetir da zai tafiyar da ita, ya kuma ba ta zangon mulki mai tsawo sa'an nan kuma ya kai mutanenta ga tudin natsira. Wani abin takaici shi ne yadda guguwar siyasa data qara murtikewa da qaratowar samun mulkin kai a shekarar 1959, da son wanzuwa har sun sa yawancin shugabanni da Sarakuna sun manta da koyarwar shugabancin Bello. A dalilin haka ne sai Gwamna ya tuna wa Sarakuna da cewa: "Adalci Shi Ke Sa Mutane Su Goyi Sarakuna"[2]

Adalilin haka ne sai Sarkin Dikwa ya yi godiya ga jawabin da Gwamna ya yi. Ya ce jawabin nan na sa abin kulawa ne wanda ya nuna manufar gwamnati sosai. Ya ce ya kamata duk 'yan Majalisan nan su kula da gargaxin nan da Gwamna ya yi, sa'an nan su goyi bayan gwamnati kan qoqarinta na kyautata Jihar nan.

Shi kuwa Atta na Igala yana so gwamnati ta koya mulkin En'e a waje ga 'yan Majalisu. Ya faxi dalilin da ya sa yaran da suka bar makaranta suke qin kama aikin En'ensu saboda qarancin albashi da kuma rashin girmama al'adu. Yana so a riqa koya haqqoqin jama'a a makarantu, sa'an nan a samu hanyoyin da za a riqa koya wa 'ya 'yan Sarakuna sha'anin mulki. Ya ci gaba da cewa idan Sarakuna suka kasa kulawa da gargaxin nan na Gwamna, to, su ba masu mulki na sosai ba ke nan. Ta haka sai su rasa amincewar mutane.

Sarkin Gwandu ya ce, idan Sarakuna suka kula da gargaxin Gwamna, to komai zai yi musu daxi ke nan. Ya gode wa Ubangiji Allah da ya sa suka zama

---

[1] GTK 26 ga Maris 1957.

[2] *Ibid.*

shugabanni, saboda haka kuma dole su yi aiki bisa adalci. Saboda aikinsu ne su riqa yin rangadi suna jin kukan jama'a, su kuma ga anyi komai bisa gaskiya. Domin ce babu abin da ya fi daxi fiye da shugabanni su riqa tafiyar da komai bisa gaskiya. Idan suka yi adalci, ba yadda mutane za su qi Sarkinsu.Ya ce maganin tafiyar da mulki sosai, shi ne wayar da kan jama'a. Ya gode wa Gwamna da faxakar da su kan abin da alhakkin da ke wuyansu.

Sarkin Kagoro M. Gwamna Awan ya taya Ministocin da aka sake zavensu murna ne, sa'an nan ya yi baqin cikin kayad da waxansu, waxanda suka yi wa Jihar nan aiki sosai. Ya roqi shugabanni su nuna soyayya ga kowa ba tare da duban bambancin addini ko qabila ba. Ya faxakar da wakilai masu zuwa taron London suyi hankali da alhakkin da ke kansu.

Sarkin Misau, ya ce ya kamata ayi qoqarin kashe cin hanci da rashawa. Don kuwa abin kunya ne idan ba a kashe zamba da lalaci kafin mulkin kai ba.[1] Gwamna Sir Bryan ya yi maganar qaratowar taron London, ya kuma umurci wakilai su zama jakadun Arewa nagari a wannan muhimmin taro. Arewa ta baiwa Taron London muhimmanci qwarai da gaske, an kuma sami haxin kai a tsakanin Majalisar Sarakuna da ta Wakilai.

Sarakuna sun taimaka gaya wajen ganin an yi ayyukan ci gaba da raya qasa da jin daxin jama'ar Arewa. A shekarar 1957, lokacin da ake qoqarin zuwa taron Gyaran Tsarin Mulki a London, sai da Sarakuna suka yi taro na musamman don su yi shawara a Kaduna. Sarakuna talatin da takwas daga cikin hamsin da xaya waxanda ke cikin Majalisar Sarakunan Jihar Arewa, su ne suka taru a *Lugard Hall* ran 21 ga Afrilun shekarar 1957, suka yi shawarwari kan maganganun da NPC, jam'iyyar da ke riqe da mulkin Jihar Arewa, za ta kai Taron London na Gyaran Tsarin Mulkin Nijeriya.

Sarkin Gwandu Alhaji Haruna, C.B.E, wanda yake shi ne Muqaddashin Shugaban Majalisar Sarakuna, shi ne ya shugabanci wannan taron. Sarakuna sun yi mahawara da shawarwari kan irin abubuwan da za su shafi Jihar Arewa, game da Tsarin Mulkin da a ke nufin yi in an je London.

Bayan an tashi daga taron, sai Mai Bedde Umar Sulaiman, wanda yake shi ne Sakataren wannan taron, ya ba da sanarwa, ya ce an jitu sosai a bisa dukkan batutuwan da za a ambata a Taron Gyaran Mulki a London. Sanarwar ta ci gaba da cewa Taron Sarakuna ya yarda gwamnatin Jihar Arewa ta karvi mulkin kai cikin shekarar 1959, amma akwai waxansu abubuwa da suka kamata a lura da su, domin amfanin Jihar Arewa. Majalisa ta zavi Sarkin Kano Alhaji Muhammadu Sanusi, da Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo, da Attah na Igala su wakilce su a Taron London.

---

[1] GTK 26 ga Maris 1957.

Jam'iyyar da ke hamayya da gwamnati a Majalisar Wakilan Arewa, wato NEPU da qawayenta sun zavi waxanda za su wakilce su a Taron London. Waxanda suka zava su ne Malam Aminu Kano, babban shugaban NEPU,da M. Ibrahim Imam, shugaban masu Adawa da gwamnati a Majalisar Wakilai da Alhaji Maito xan Jam'iyyar ITP-AG.

Malam Aminu Kano shi ya ba da wannan sanarwa. Sa'annan yaci gaba da cewa Jam'iyyar Action Group a can Jihar Yamma za ta sanya Mr. Olawoyin sakataren Action Group a Arewa cikin wakilai a masu zuwa Taron London.[1] Daga qarshe an ba da sunayen waxanda za su tafi wannan babban taro.

gwamnatin Jihar Arewa ta bayyana dukkan sunayen wakilai, da mashawartansu,da masu zuwa kallo,waxanda za su je London, domin sha'anin taron da za a buxe na Gyaran Tsarin Mulkin Nijerya a ran 23 ga Mayun shekarar 1957. Ainihin wakilai, su goma ne. Mashawartansu, ko kuwa muqaddasansu guda biyar. Waxanda za su je kallo wato "observers", su shida ne. Duk gamawa, Jihar Arewa za ta tura wakilai guda ishirin da xayake nan zuwa London.

Wakilan NPC su ne: Firimiya Alhaji Ahmadu Sardauna, da Alhaji Muhammadu Ribaxu, Ministan Nijeriya na Ma'adinai da Lantarki, da Madawakin Katsina Alhaji Isa Kaita, Ministan Jiha na Arziqin Qasa, da Alhaji Muhammadu Inuwa Wada, Ministan Nijeriya na Fidaburdi, da Makaman Bida Alhaji Aliyu, Ministan Jiha na Ilimi, Ciniki da Sana'o'i.

Wakilan NEPU da qawayenta su ne: Malam Aminu Kano,babban shugaban NEPU, da M.Ibrahim Imam na jam'iyyar *Borno Youth Movement*, wanda yake shi ne shugaban masu hamayya da gwamnatin NPC a Majalisar Wakilai.

Wakilan UMBC su ne: Mr.Tarwan S. Tarka, babban shugaban UMBC kuma memba na Majalisar Nijeriya daga qasar Tiv ta lardin Binuwai. Wakilan Sarakuna su ne: Alhaji Muhammadu Sunusi, Sarkin Kano, Minista mai ba da Shawara, da Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo, Minista mai ba da shawara.

Mashawartan Wakilansu ne: M. Abba Habib, Ministan Jiha na Kamaru ta Arewa, da Fidaburd,kuma Janar-Sakatare na NPC, da Wazirin Barno Shettima Kashim (NPC), da Mr G.U. Ohikere, Ministan lafiyana Jihar Arewa, kuma xan jam'iyyar *Igbirra Tribal Union*, qawar NPC, da Mr. Patrick Dokotri Janar-Sakatare na UMBC, kuma memba na Majalisar Nijeriya daga Jos, da Atta na Igala Aliyu Obaje, xan Majalisar Sarakuna.

'Yan kallo su ne: Mr. Michael Audu Buba (NPC), Sakataren Majalisa na Ministan Ciniki da Sana'o'i, da Alhaji Isa Haruna, babban shugaban NPC na lardin Qasar Kuza, da Mr. J. C. Obande (NPC) memba a Majalisar Nijeriya daga Binwai, da Mr Emmanuel Olanrewaju (NPC) memba na Majalisar Nijeriya daga Ilori, da M. Abdul Ganiyyu Razaq, lauyan NPC, da Alhaji sulaimanu Maito,

[1] GTK 26 Afrilu, 1957

shugaban Ilorin Talaka Parapo kuma memba na Majalisar Wakilan Arewa daga Ilorin, shi ne zai wakilci NEPU da qawayenta.

A wannan taro ne za a kwance a tsettsefe abubuwa sosai da sosai, saboda haka ne babu lardin da bai samu a qalla mutuminsa guda wanda za shi taron London ba. Misali, in an bi filla-filla, za a ce Sakkwato ta sami mutuminta guda. Shi ne Firimiya da kansa. Kano ta sami mutanenta uku. Su ne Sarkin Kano, Alhaji Inuwa Wada da Malam Aminu Kano. Adamawa, Alhaji Muhammadu Ribaxu. Katsina, Sarkin Katsina da Madakinsa Alhaji Isa Kaita. Barno, Wazirin Barno, da M. Abba Habib, da Malam Ibrahim Imam. Neja, Alhaji Aliyu Makaman Bida. Kabba, G.U Ohikere, da Atta na Igala Aliyu Obaje. Qasar Kuza, Michacl Audu Buba, da Alhaji Isa Haruna, da Patrick Dokotri. Binwai, T.S Tarka, da J.C Obande. Ilori, Mr Emmanuel Olanrewaju da Alhaji Sulaimanu Maito. Zariya, M. Abdul Ganiyu Razaq.[1]

Har ila yau idan anbi wannan lissafi, za a ga Larduna goma sha-xaya ke nan. Saura Lardi guda, wanda ba a ga sunansa ba, balle a ga mutuminsa da za shi London. Wannan Lardi, shi ne Bauci. Akwai mutuminsa kuwa cikin masu zuwa Taron London. Muhimmin mutum kuwa, shi ne Malam Abubakar Tafawa Valewa, Ministan Nijeriya na Sufuri. Shi zai wakilci gwamnatin Nijeriya ne. Amma dai Bauci ma ta na da mutumin ta cikin taron. Masu ba shi shawara M. Dipcharima da M. Bello Xandago.

A shekarar 1957 bayan taron London aka kafa Majalisar Sarakuna ta jiha a Kaduna. An ba wannan Majalisa, alhakkin zaven Sarki da naxinsa, tare da horo da qarin girman Sarakuna kamar yadda ya kamata. Firimiyan Arewa, Sir Ahmadu Bello ne ke zama Shugaban Majalisa a duk lokacin zamanta.[2] An qara samar da Majalisar Wakilai don su tafi kafaxa da kafaxa da juna. A wannan lokaci kuwa Majalisar Sarakuna na ba da gudunmawa dai dai da na Majalisar Wakilai a duk harkokin gwamnati.

Shekarar samun 'yanci na qaratowa, 'yan siyasa kuma na qara xaukar matakan ganin kishiyar 'yan Majalisar Wakilai na dushewa domin kada mulkin Mulukiya ya yi tasiri a Nijeriya. Saboda haka sai aka sami sauye-sauye a tsakanin shekarar 1955 zuwa 1959 a tsarin mulki a Arewa. A shekarar 1957 ne aka zartar da umarnin da kwamiti xin da Hudson suka bayar a shekar 1954 wato *Hudson Committee Report of 1954*. Wannan kwamiti ya ba da umarni ne da a canza matsayin Sarakuna a Majalisa daga masu ikon zartarwa wato *Emirs-In-Council* zuwa matsayin masu zama a majalisa kamar kowa abin da aka kira *Emirs and*

---

1 GTK 3 ga Mayu, 1957

2 Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isiyaku*, shafi na 338

Council, inda zartar da komai na buqatar jefa quri'a. Ita wannan doka sai ta zama wata hanya ce da ta regewa Sarakuna zartar da hukunci, a harkokin mulki a jiha.[1]

Zartar da wannan shiri ne ya karya qashin bayan muxlaqin mulki ya kuma karkata aqalar Arewa zuwa ga Jamhuriya. Saboda ba za a ci nasarar samun mulkin Jamhuriya bisa mulkin mulukiya ba sai an rusa abin da 'yan Siyasa suka kira muxlaqin mulki. Dokar Emirs and Council da aka zartar, shi ya rusa Arewa ya kuma ci gaba da zaizaye qarfinta da tasirinta a harkokin Nijeriya har yanzu.

Don kuwa shi ne matakin farko na dakile ci gaban mulkin Mulukiya. Duk da haka bayan Taron London da aka yi ne, sai rahoton wannan taro ya ba da umarnin kafa Majalisar Duba Sarakuna. Amfanin wannan majalisa ya sanya tilas a qwarzantata ta kula da halin Sarakuna.

Majalisar Duba Halin Sarakuna

Za a kafa wata Majalisa ta Sarakuna wadda Gwamna ke cikinta, kuma a sami a qalla Sarakuna biyu ko kada su fi huxu daga Majalisar Gudanarwa, Firimiya da kuma Sarakuna huxu daga cikin 'yan Majalisar Sarakuna. Majalisun nan da za a kafa za a ba ta ikon yarda da naxin Sarakuna, da tabbatar da shi, darajarsu da kuma tuve su, ko xauke su daga wani wuri zuwa wani wuri a Jihar nan a muqaminsu na Sarakuna ko kuma 'yan Hukumar En'e.

Wannan yana cikin rahoton taron gyaran Shirin Mulkin Nijeriya wanda ya fito a cikin watan Afrilun shekarar 1957. A Majalisar Sarakuna ta Jihar Arewa, Gwamna Cikin Majalisa ne zai naxa shugaban Majalisar Sarakuna da muqaddashinsa daga cikin 'yan Majalisan Sarakuna. Shugaban Majalisar Wakilai za a riqa kiransa kakaki, wato *Speaker*, mataimakinsa kuma za a riqa kiransa Mataimakin Kakai, wato *Deputy Speaker*.

Majalisar Gudanarwa ta Jihar Arewa za ta kasancewaxanda ke cikinta su ne Gwamna, da Antone-Janar, da Wakilan da ba su gaza goma sha-biyu daga Majalisar Wakilai ba, xaya daga cikinsu ya zama Firimiya, kuma a qalla Sarakuna biyu ko kada su fi huxu daga Majalisar Sarakuna.

Shirin mulkin nan zai ba Gwamna Cikin Majalisa iko a kowane lardi a Hukumar Lardi wadda za ta kasance tana da Majalisarta ta Lardi da Hukumar Lardi. Wanda zai shugabanci Hukumar Lardi ya zama ma'aikacin gwamnatin jiha ne. Shi ne babban mai iko da za a riqa kiransa *Provincial Administrator*.

Taron ya yarda kada a xauki wata shawara a yanzu na ko za a buqaci kiran wani taro a shekarar 1959 don a shirya samun mulki Jihar Arewa, wanda zai yi dai-dai da abin da aka yarda da shi don Jihar Yamma da Gabas.

---

[1] Usman Dalhatu, *Malam Ja'afaru Xan Isiyaku* , shafi na 346

Gwamna-janar ne zai naxa Firayim Minista na Nijeriya wanda a ganinsa 'yan jam'iyyarsa su suka fi yawa a Majalisar Nijeriya. An yarda don kada abin ya kawo ruxani a qasashen waje muqamin Firayim Minista ya zama an qayyade shi a gwamnatin Tarayya ne kawai, a jihohi kuma a riqa amfani da muqamin Firimiyoyi. A wannan taro kuma an xauki matsayi akan sojojin Nijeriya. Taron ya yarda cewa daga 1 ga Afrilun shekarar 1958 Majalisar Sojoji ta Ingila da ke da iko kan sojojin Nijeriya za su bar zama suna da iko kansu.

An yi shawara kan maganar sanya sha'anin 'yancin 'xan-Adam cikin Shirin Mulki. An yarda da tanadi wannan, amma saboda rikitarwar wannan muhimmiyar magana da farko mashawartan Sakataren Qasashen Ingila kan shari'a za su shirya yadda za a sanya shi cikin Shirin Mulkin. Idan aka shirya shi za a aika wa dukkan gwamnatin Nijeriya, sa'an nan a duba shi a taron Shirin Mulki da za a ci gaba da shi ba da daxewa ba.Taron ya yarda cewa tun da yake maganar duba kan iyakar qasa masu binciken matsalar qananan qabilu za su duba shi, to, ba a tava maganar a wannan taron ba.[1]

A shirin murje mulkin *Indirect Rule* ya tafi da dimukuraxiya ba a maida Sarakuna fifa-iya-koma baya ba, don su ne jigon ci gaban jama'ar Arewa. Don haka a matsayinsu na Mashawarta, sai aka bar su a matsayin jijiyoyin Siyasa a Jihar Arewa da Jihar Yamma. Domin *Indirect Rule* ne zanganniyar dake riqe da su. Da zuwan wannan Shiri na Raya Qasa, sai suka jajircewajen ganin Arewa ta samo kaso mai tsoka a wannan garavasa. A wancan zamani kuxin da Arewa ke samu bai wuce fam miliyan takwas a shekara ba. Qwamfa! Sai ga fam miliyan 55 za a kashe wajen gyaran Nijeriya. Ka ga Sarakuna ba za su koma gefe suna kallon ana watanda da kason Arewa ba, tilas su tsaya tsayin daka su ga an kashe kason kuxin Arewa ta hanyoyin da suka dace. Sarakuna ke kan gaba wajen kishin ganin Jihar Arewa ta kai ga tudun na tsira a wannan zamani. Saboda sun sa ido sosai don wannan gagarumin shiri ya kai ga nasara.

Dalilin haka ya sa suka shiga yin taro da 'yan Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna su na masu tattauna matsalolin Arewa da yadda za a yi maganinsu. Suna kuma ba da shawarwari tare da sa ido kan yadda ake samun kuxin shiga da yadda ake kashe su. Sarakuna na kuma taimakawa wajen samar da kuxin shiga daga jihohinsu a bisa tsarin En'e, suna kuma taimakawa wajen zaman lafiya da ci gaban jama'arsu. Saboda waxannan ayyuka da wasu makamantansu ya sa kowane gwamnan Kaduna ke zaman taro da Majalisar Sarakuna da 'yan Majalisar Wakilai. Saboda haqqin Gwamna ne kashe kuxaxen jiha da gwamnati ta samu, wannan ya sa ya kan zo taro ya yi bayani dalla dalla yadda ya kashe kuxi da kuma abubuwan da aka yi da su. Zuwan Sarakuna taro da Gwamna, ya qayatar da Kaduna ya kuma ba ta wata izza mai ban tsoro da sha'awa da xaukaka. Da fika-

[1] GTK 12 ga Yuli, 1957

fikan Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai, Arewa ta fara tashi tana kuma bunqasa.

Ko da yake an sami ci gaba sosai amma sai Sarakuna suka taka ruvavvar qaya, don kuwa 'yan Majalisar Wakilai sun xauke su kishiyoyi a harkar mulki. Don haka ne dokar Sarki da Majalisa *Emirs and Council* ta fara figewa Majalisar Sarakuna fiffiken tashi.

A ranar 20 ga watan Janairun shekarar 1947, Majalisar Wakilai ta Arewa ta fara zamanta na farko. Ga abin da Sir Bryan ya ce game da wannan zama: "Abin sha'awa. Ga mu, mu Razdantai tare da tsofaffin abokanmu, ma'aikatan En'e, za a karanta sabon shafi na shirin qasar nan. A rana ta biyu aka zavi mutum biyar waxanda su ne za su wakilci Arewa a Majalisar Nijeriya ta Lagos."[1]

To bayan wata biyu sai aka kira taron Majalisar Dokoki ta Nijeriya. Majalisar Sarakuna ta Arewa, sai ta tura wasu Sarakuna, su walkice ta a wannan taro. A wannan taro ne M. Abubakar T. Valewa, Wakilin Bauci kuma xan Majalisar Sarkin Bauci, aka ce ya jagoranci rundunar Arewa inda ya yi wannan kalami: "Waji bi ne a baiwa jama'ar Arewa da masu da kansu su shirya mai fisshe su, kuma wajibi ne a zana iya kancin mulkin Sarakuna. Kowa ya san iyakacin matsayinsa."[2] Daga wannan lokaci ne 'yan Siyasa suka fito fili daga yaqin sunquru, suka riqa kai wa muxlaqin mulkin Sarakuna naushi da tokara, ba don komai ba, sai don a fasa shi su sami abin dafawa.

Wannan mashahurin mutum shi ne ya fara kaxa gangar yaqin qwatar girma da `yanci wadda ta tada hankalin jama'ar qasarsa. A wannan yunquri ne 'yan Siyasa a Majalisa suka fito gadan-gadan wajen yaqin qwatar 'yanci daga Sarakunansu. A wannan lokaci mulkin Sarakuna na samun mummunar suka daga 'Yan Arewa masu ilimin zamani. Yana kuma samun zagon qasa daga Turawan Mulki. Waxannan guguwoyi ne suka taso da qarfi don su tuge Sarakuna, tutocin Shehu Mujaddadi.

Tuge Tutocin Shehu Mujaddadi

`Yan Arewa masu ilimin zamani sun taso da fahimtar cewa `yan Kudu da Sarakunan Arewa su ne qalubale a garesu. Abin lura a nan shi ne masu ilimi a Arewa, wato 'yan Siyasar Farko, suna yaqin Qwatar girma daga 'yan Kudu, har ila yau suna yaqin Qwatar 'yanci daga Sarakunansu duk a lokaci guda. Turawan mulki ne suka qulla wannan qiyayyar tsakanin Sarakuna da 'yan COBA a lokacin da Mulkin Mallaka ya yi qamari sosai. Yaqi da Majalisar Sarakuna sai ya varke ya kuma yi qamari saboda guguwar ba da mulkin kai, na kaxawa sosai. To, wanne ne ba wanne ne ba! Wannan rikirkitaccen lamari sai ya zame masu yaqin Qwatar

---

1 GTK 12 ga Yuli, 1957.

2 Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 43.

Kansu. Wannan ya tilasta 'yan Boko su tafi a guje, jama'arsu kuma na tafi a sannu. A kalamin M. Abubakar T. Valewa, da ya yi ya nuna cewa tilas a yi wa mulkin En'e, gyara don su ma 'yan Siyasa su sami makama, don haka ne ma ya ce, "Wajibi ne a zana iyakacin mulkin Sarakuna." Sa'annan ya fuskanci yaqin qwatar girma da wannan bayani:"Ba mu son mulkin kai yanzu, za mu bixe shi sa'adda komi ya nuna. Ba ga roqon mulkin kai za mu tsaya ba, za mu ma yaqo shi ne, idan lalama ba ta bayar ba. Amma idan Ingilishi suka kuskura, suka fita Nijeriya yanzu-yanzu, to mu mutanen Arewa, za mu ci gaba da kabbararmu ta yaqi, muna tafe muna cin qasashen Kudu har sai mun kai Teku. Kamar yadda dai muka fara, Turawa suka zo suka tsare mu."[1] Wannan kalamin qarshe sai ya zama shi ne mafi haxari ga wannan mashahurin mutum. Domin kuwa a wannan lokacin 'Yan Kudu na neman hanyar da za su maida martani da 'yan Daular Usumaniyya, waxanda suka kai farmaki qasashensu da niyyar sai sun dangane da bakin teku. Bugu da qari 'Yan Kudu na qiyayya da Sarakuna ne saboda su ne Wakilan Shehu Mujaddadi a wannan zamanin.

A lokacin da M. Abubakar Tafawa Valewa, ke wannan magana wadda ta girgiza majalisar, ya yi tane saboda shirin da aka yi da NCNC ta wakilci Arewa a wajen ba da mulki a shekarar 1956. A dalilin haka ne ya fito fili ya ce, 'yan Arewa ba su yarda N.C.N.C ta wakilce ta ba. Ya kuma qara da cewa Arewa mazaje ne, ba su buqatar wani ya yi masu yaqin qwatar girma.[2] A wannan lokaci 'yan Kudu suna gudu ne zuwa qwatar mulkin kai, 'yan Arewa kuma suna tafiya a sannu. Don haka sai aka ba da shawara Jami'yyar NCNC, ta wakilci Arewa. Amma sai Arewa ta qi, ta ce, "kifi na ganinka mai jar koma!" A wannan taro ne wannan mashahurin Wakilin Lardin Bauci, ya yi arangama da jam'iyyar Dr. Nnamdi Azikiwe. Shi kuwa Sardauna da Cif Obafemi Awolowo ya yi tasa arangamar a wani zama da Majalisar ta yi.

A wani taron Majalisa, sai wani xan jam'iyyar *Action Group* wadda Cif Awolowo ke wa jagora, ya takalo maganar nan da 'yan Arewa ba so su su ji, saboda ba su shirya ma ta ba, ya ce: "Ina roqon wannan majalisa ta karvi ra'ayin cewa wannan qasa ta Nijeriya, ta sami Mulkin kanta, a cikin shekara ta 1956".[3] Tunda ba a zo don wannan batu ba saboda haka sai Mutanen Arewa su ka ce suna so a ba su damasu koma gida su shawarci jama'arsu. Amma sai Cif Awolowo, ya yi wuf ya ce: "Waxanne jama'a za a ce a koma gida a ji ra'ayinsu? Wane ra'ayi gare su. Su banda ra'ayin bixar abincinsu, da bixar wurin kwanansu, da bixar tufafinsu . . . ?" Yaci gaba har ya ce: "Da qasusuwan Mujaddadi Shehu Usman

---

1 Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 43.

2 *Ibid*.

3 Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 43.

Xanfodiyo za su ji wannan magana daga bakin xaya daga cikin jikokinsa, da baqin ciki ya sanya qasusuwan nan sun girgiza"[1] Kafin ya gama magana, sai Sardauna Gamji Xan Qwarai ya miqe, yana kyarma, ya ce:"Oda-Oda! Ka da in sake jin an kira sunan Shehu Mujaddadi Usman Xanfodiyo, a haka, a wannan majalisa."[2]

A dalilin haka sai duk wakilan Arewa suka yi caa gava xaya, suna goyon bayansa suna cewa, "Haka nan ne, haka nan ne!" Abokan hamayya suma sai suka karva, "Me zai hana, me zai hana?" Tun kafin samun mulkin kai, 'yan Kudu ba su xauka Arewa ta isa ta ja da su ba. Abin da ake qokarin yi shi ne a hanzarta samun mulkin kai, don 'yan Kudu su mallake 'yan Arewa baki xaya. A kullum a shirye suke su xau yaqin darkake Arewa daga bakin Teku wanda zai dangane da Sahara. Ba sa voye qoqarinsu na neman mallake Arewa. Saboda haka ne wannan hali ya tilastawa 'yan Arewa xaukar gwagwarmayar qwatar girma. Amma gwagwarmayar qwatar 'yanci da shugabanin siyasa suka ce suna yi sai ya yi birgirmar hankaka ya koma qiyayya da Sarakuna a voye. Saboda Son kai ya rinjayi so da Kishin Arewa. A wannan lokaci ne garwashin wutar qiyayya da Sarakuna da aka cunkusawa 'yan COBA ta fara ruruwa.

Mulkin Sarakuna ya daxe a Arewa. Almisali, qasar Kano da lardun Barno sun sami fiye da shekaru dubu suna ganin mulkin Sarakuna iri-iri. A ranar Litinin 2 ga Fabrairun shekarar 1959, Sarkin Kano Sir Muhamadu Sunusi ya buxe qasaitaccen bikin shekara dubu (1000) da kafa birnin Kano.[3] A wannan rana ce mutane kusa da dubu xari biyar (500,000) suka hallara a filin wasa don shagalin wannan biki na shekara dubu da kafuwar gidan sarautar wannan birni. A wannan rana ce da misalin qarfe takwas na safe, manyan baqi suka hallara a wajen wannan biki.

Wanda ya fara zuwa shi ne Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa, Firayim Ministan Nijeriya, daga nan sai Gwamna Janar na Nijeriya, Sir James Robertson da Uwargidansa, Lady Robertson da Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, da gwamnan Arewa Mai Riqo, Mr. A.T. Weatherhead da Sarakuna, da Hakimai da Dagatan Qasar Kano. [4] Dubban jama'a sun hallara suna murna da wannan rana ta cika shekara 1000 da kafa birnin Kano, Jalla babbar Hausa.

Akwai qasashe da yawa da suka yi fiye da shekara 1000 da kafuwa a Arewa. Saboda haka mulkin Sarkuna a Arewa daxaxxe ne. Bugu da qari mulki ne da ya tasirantu akan jama'ar wannan jiha mai bambanci da ban mamaki. Jihar Arewa ba kamar Jihar Gabas take ba wadda sai a shekarar 1919 aka yi qoqarin koyar da

---

1 Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 43.

2 *Ibid*.

3 The Nigerian Citizen: *Kano Festival*, February 4, 1959

4 *Ibid*.

mulkin Sarakuna a kan jama'ar wannan jiha. Har ila yau mulkin Sarakuna ya qara samun kakkyawan fasali da inganci, a zamanin Shehu Mujaddadi wanda ya kawo mulkin Fulani, kusan shekaru xari kafin zuwan Turawa.

Da zuwan Turawa a farkon shekarar 1900, sai suka kawo sauye-sauye da za su dace da da Mulkin Mallaka. A daular Turawa sai aka samu larduna goma sha-uku (13), kamar yadda Fulani suka tafiyar da nasu mulkin. Amma kuma sai aka qara Qasashen Sarakuna daga goma sha-uku (13) zuwa tamanin da takwas (88). Aka kuma qirqiro En'e-En'e qarqashin Di'o-Di'o da qasashen Sarakuna guda sittin da tara (69). A bisa tsarin har ila yau aka tsaga qasashen a matsayin gundumomi a inda aka samu gundumomi xari biyar da hamsin da biyu (552).[1]

Ko da yake Turawa sun yi ma wannan tsarin mulki gyaran fuska amma sai suka yi qoqarin su raba hanta da jini. A wannan tsarin Mulkin Mallaka sai aka maida Sarki qarqashin Razdan wato an nesanta talaka daga Sarkinsa. An yi haka ne saboda a tafiyar da mulkin jama'a ta kan Sarakunansu, ga Sarki a kan karagar mulki amma iko na hannun Razdan ko Di'o. Wannan tsari sai ya baqanta Sarki ga jama'arsa. Saboda qoqarin Sarki sai ya koma na farantawa Razdan rai ne amma ba talakawansa. Duk kuma abin da Razdan ko Di'o ya zartar ta kan Sarki zuwa ga jama'a, mai kyau da mara kyau duk sun rataya ne a wuyan Sarki. Saboda haka sai Razdantai su baqantawa jama'a Sarakuna kuma su xauke laifukansu. Matsayinn da Di'o da Razdantai za su bari bayan *Indirect Rule* shi 'yan Siyasa suke qoqarin karva da qarfi da yaji.

A qarshen mulkinsu sai Turawan mulki suka haddasa gaba a tsakanin Sarakuna da 'yan Siyasa. Saboda in an tsotse lemo sai a yar da fatan. Turawa ba su shimfixa maqarqashiyar rusa mulkin Sarakuna ba sai bayan sun gama amfani da su. Domin haka ake cewa, baka san tsiyar Bature ba sai ya tashi zuwa gida. Turawa sun bar Arewa ne bayan sun haddasa gaba da qiyayya a tsakanin Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai ta 'yan Siyasa. A dalilin haka ne 'yan Siyasa suka xauki gwagwarmayar tuge jijiyoyin mulkin Sarakuna da suka yi fiye da shekara dubu da kafuwa. Domin neman su zauna a makwafin Turawan Mulki. Su kafa muxlaqin Mulkin Siyasa na *Wahadahu La Sharika Lahu*.

A qoqarin 'yan Siyasa na maida Arewa ta dai-dai ta sahu da Jihar Gabas sai mulkin Sarakuna a Arewa ya zama Gwaxayi ba saranka ba janka! A duk lokacin da suka yi qoqarin tuge wannan mulki na gargajiya sai su kasa. Saboda har yanzu a mulki na hannun 'yan Siyasa, amma jama'a kuma na hannun Sarakuna. Tun daga 1960 har yanzu 'yan Siyasa sun kasa haxa iko da goyon bayan jama'a wajen mulkinsu. Saboda haka 'yan Siyasa na tsoron Sarakuna ne ba domin komai ba sai don gudun kada su karve masu iko. A halin da ake ciki a yanzu ci gaban Arewa sai ya yi gaba ya yi baya, yana tafiyar kura saboda rashin jituwa da ke tsakanin

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa* shafi na 301

'yan Siyasa da Sarakuna a Arewa. Wannan qiyayya da hamayya ce, Arewa ta gada daga Mulkin Mallaka. Shi ne ke zaizaye wa Arewa izza da buwaya a Nijeriya. A zamanin Siyasar farko 'yan Siyasa na yaqi ne da Ci Uku (Zalunci, Lalaci da Jahilci) da suka ci Arewa. Amma a wannan zamanin kuwa akwai Tarko Uku da suka kama Arewa waxanda ba a farga da su baballantana a xauki yaqi da su.

Tarko Uku da Suka ci Arewa

Tirqashi! A lokaci guda 'yan Siyasa sun xauki gwagwarmayar yaqi a cikin Arewa da yaqi a wajenta. A cikin Arewa suna yaqin qwatar 'yanci da Sarakunan su da kuma Yaqin Qwatar Girma da 'yan Kudu. A wancan lokaci suna tsoron kada Sarakuna su yi qarfi har su kai qasar ga mulkin Mulukiya. Don haka sai suka shiga yaqi da Sarakunansu ta qarqashin qasa suka kuma riqa yin abubuwan da za su zaizaye qarfin Sarakuna domin su sami nasara da galaba akan su. Turawa kuma suna taimaka masu a fakaice.

Wajen yaqin Qwatar Girma da Kudu kuwa sai suka qara kururuta gaba da hamayya da 'yan Kudu tare da qin neman yin abota mai kyau da xorewa da wata jam'iyya daga Kudu musamman jam'iyyar AG., don su nuna wa jama'a ta hanyarsu su ne kawai jama'ar Arewa za su sami sa'ida, da mafita da kaiwa ga nasara.

Idan aka duba wajen Qwatar 'Yanci kuma sai aga, 'yan Siyasar Farko sun rage qarfinsu sosai a yaqin kwato 'yancinsu daga Sarakuna. Domin haka ne qarfinsu ya raunana matuqa saboda ci da zuci da suka nuna wajen neman mulkin Arewa. Sir Bryan, ya ba da haske akan qwanjin da masu ilimin zamani a Arewa ke wa Mulkin Sarakuna, inda ya ce: " To, ba girin girin ba dai ta yi mai-kura ta saci ganga. Abin da mutane ke duba ke nan a gare mu. A cikin shirin mulkin Nijeriya ta Arewa, babban abin da kowanne xan Arewa mai ilimi ya tsana, shi ne wata daraja muxlaqan wadda mulkin Arewa ya baiwa Sarakuna. Shi ne muka ce da Turanci a ke kira *Sole Native Authority*. Ma'anarsa shi ne, cewa doka ta baiwa Sarki muxlaqin mulki *Wahadahu La Sharika Lahu*. Ko da shi ke a yadda abin ke tafiya, kowane Sarki yana shawara da majalisa. Amma dai tun da yake doka ta ba shi wannan muxlaqin mulki ko bai yi aiki da ita ba, duk da haka ya dai san tsarin mulkin ya ba shi wannan iko."[1]

'Yan Arewa masu ilimi wato 'yan Siyasa sun tsani wannan muxlaqin mulki kamar yadda suke qin ba da mulkin kai a shekarar 1956, wanda zai baiwa `yan Kudu damar mulkin Nijeriya da mallakar Arewa baki xaya. Saboda haka idan ana son a kafa siyasa, ya zama tilas a rusa shi. Wannan qiyayyar kuwa tun daga kwaleji suke fitowa da ita garwashin wutar wannan qiyayya sai qara ruruwa yake a kullum. A wannan lokaci sai hankalinsu ya rabu guri biyu wajen: Qwato Girma

[1] Alhaji Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 63

daga 'yan Kudu da Qwato 'Yanci daga Sarakuna. Abin takaici sai suka fuskanci waxannan abubuwa biyu a lokaci guda. Wannan hali, ya rage masu qarfi sosai, musamman idan aka yi la'akari da cewa, Arewa ba ta da isassun ma'aikata da masu ilimi. A cikin wannan mummunan hali, Sarakuna na tsaka mai wuya. Sai wasu 'yan boko suka haxa kai da 'yan Kudu don su cimma muradinsu. Sarakuna suna gaba kura baya siyaki a tsakanin Turawan mulki da talakawa. A cikin wannan hali kuma sai suka taka ruvavviyar qaya – 'yan Arewa masu ilimi. Su kuma masu ilimi, suna cikin zulumin mallaka daga 'yan Kudu, a lokacin da suke fafitikar qwatar 'yanci daga Muxlaqin mulki a Arewa. Duk al'amuran sai suka nemi su dagule! A maimakon shugabanni su duqufa wajen gina al'ummarsu a kan harsashin ilimi da sana'a sai suka shagala wajen neman mulki da muqami.

Abin da ya kamata su yi shi ne su haxa kai da Sarakuna har na tsawon wani lokaci inda suka qara qarfi sosai ta yawan masu ilimi da ma'aikata. Amma saboda gaggawan son mulki sai suka karya al'amari amma ba a kan gava ba. Amma akwai masu hankali da natsuwa a cikinsu waxanda ba su ga fa'idar yaqi da Sarakuna ba.

Ana maganar yaqi da mulkin Sarakuna, sai maganar qananan qabilun Arewa waxanda suke ba Musulmi ba ta taso. Su waxannan qabilu su ne suka sami isasshen ilimi a tsarin bayar da ilimin boko a Arewa, saboda a nan gaba su ne za su riqe mulkin Arewa, a wani shiri na "kyawon rawa na gaba ya koma baya" da Turawa suka shirya. A dalilin haka ne, Sir Bryan ya ba da shawarwari da a ba su Minista, a kuma ba shi aikin yi, idan ana son Arewa ta zauna xinke. A wancan lokacin qananan qabilun Arewa ba su da qarfi, amma da shirin ya yi tasiri yanzu suke faxa aji a sassa da dama a Arewa. An raba kan Musulmi da Kirista a Arewa, a bisa tsarin nan na Turawa, *Divide et impera* wato *Divide and Rule*. Haka kuma wannan mummunan tsari ya qulla gaba da hamayya tsakanin Sarakuna da `yan boko ya kuma assasa qiyayya tsakanin Musulmi da Kirista. Saboda haka sai ci gaban Arewa ya riqa tafiyar kura.

Turawan Mulki ne suka qirqiro da siyasa da Sarakuna saboda mulkin *Indirect Rule* ya tafi sosai. Amma irin wannan samfurin mulki bashi a Kudu. A kudancin Nijeriya ilimi ya kawo wayewa tare da bijirewa Turawan Mulki, waxanda suna ji suna ganin jama'ar da ta qarbi addininsu wato addinin Kirista ta kuma qarbi halaye da xabi'unsu, su ne kan gaba wajen korarsu a Nijeriya. A dalilin haka sai tsoron kada ilimi ya sanya 'yan Arewa su bi sawun 'yan Kudu wajen qoqarin kawo qarshen Mulkin Mallaka a Nijeriya da gaggawa. Tsoron butulci yana xaya daga dalilan hana Arewa ilimi mai yalwa da amfani.

Domin Turawa sun fi tsoron 'yan Arewa saboda nagarta da haziqanci da gogewarsu a sha'anin mulki. Babban tsoron da suke yi a wancan zamani shi ne kada Arewa ta bi sawun qasar Indiya wadda ta sami 'yancinta a shekarar 1947. A kuma take-taken Arewa tana iya 'yanke wa Turawan Mulki kaba, don su bar

wannan qasa da gaggawa. Turawan Ingilishi mutane ne masu tsinkayar al'amari domin haka sai suka xanawa Arewa tarkuna uku: biyu a ciki xaya a wajenta.

Duk wanda ya yi nazarin yadda majalisu biyu, Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai ke gasa da juna wajen yin ayyukan ci gaban Arewa, zai hangi cewa a 'yan shekaru masu zuwa qasar Arewa za ta buwaya ba a Nijeriya a Afirka baki xaya. A tsarin Mulkin Mallaka kuwa wannan ba ta savuwa saboda haka sai aka kafa wa Arewa wani tarnaqin hanata ci gaba a tarkon farko.

A tarkon farko an yi amfani da ilimi da masu ilimi wajen hana Arewa ci gaba. A wajen ilimi sai aka baiwa Arewa ilimi irin nata na Jihar Arewa, na koyar da da halin gaskiya da riqon amana, amma ba ilimin Kimiya da Fasaha ba. An daxe Turawa na wasan kura da sha'anin ilimi a Arewa. Sai a shekarar 1940 'yan Arewa suka gane a zahiri Turawa yaudarar su suke yi kawai amma ba ilimi suke ba su ba. Turawan sun yi haka ne don gudun kada su maimaita kuskurensu da suka yi a qasashen bakin teku. To, waxanda suka karvi addinin Kirista ma sun yi masu bore ballantana waxanda sai da yaqi aka mallake su.

Duk da ilimi jeka-na-yika da suka baiwa Arewa sai da suka qara wa wannan tarnaqin hana ci gaba qarfi. Saboda kada masu ilimin Arewa su yi koyi da 'yan Kudu wajen yiwa Mulkin Mallaka bore da tawaye sai suka haddasa gaba tsakanin masu ilimin zamani da Sarakunansu, a wani tsarin mulkin raba kan jama'a don a sami sauqin mallakarsu.

A shekarar 1939, Shugaban kwalejin Katsina, Mr. E. L. Mort ya qirqiro da wata hanyar ta ba da shawarar kafa qungiyar Tsofaffin Xaliban Kwaleji wato *College Old Boys' Association* (COBA).[1] Kafin kace kwabo wannan shawara ta samu karvuwa hannu bibbiyu daga Cif Kwamishina Mr. Theodore Adams. Saboda haka sai aka aika da saqo ga duk manyan jami'an ilimi akan wannan shiri, a ran 29 ga Yunin shekarar 1939.[2]

To, abin nema ya samu. A tsakanin ranar 25 zuwa 27 ga Yuli na wannan shekara har 'yan Kwaleji arba'in da huxu sun hallara a harabar kwalejin Kaduna. Akasarin waxanda suka amsa wannan kiran kafa qungiyar kuwa Malaman Elementare da Midil ne waxanda suka zo daga larduna goma sha-biyu amma banda lardin Filato. Saboda lardin Filato baya cikin wannan tarko, amma kuma yana cikin tarko na biyu.

A shekarar 1940 aka qaddamar da COBA. To, da wace manufa? A wannan shiri ne aka sauya wa masu ilimin Arewa manufa aka kuma karkatar masu da alqiblarsu. Dalilin kafa COBA shi ne don a samu a cunkusawa 'yan qungiyar qiyayya da Sarakunansu amma ba da Turawan Mulki ba. Saboda guguwar siyasa

---

[1] NAK/MIN/DDN/1845: Principal Kaduna College to all Senior E. O., College Circular No. 159/1, 29 June 1939.

[2] *Ibid*

da ta so ma qaxawa, kada 'yan Kudu da 'yan Arewa su haxa kai don su yiwa wa Turawan Mulki bore domin kuwa a wancan zamani 'Yan Kudu na neman haxa geza da 'Yan Arewa don a cimma wannan manufa. Wannan ya tada hankalin masu mulki saboda haka sai suka xauki matakin maganinsa. A wannan shirin idan 'yan Kudu suna faxa da Turawa, to, 'yan Arewa su riqa faxa da Sarakunansu. Kan 'Yan Arewa zai rabu biyu ke nan. Matuqar akwai rashin jituwa va za a sami haxin kan da za a kori Turawa ba. Wannan shiri ya yi tasiri so sosai tarkon farko ya kama yadda ake so. Turawa sun yi farraqu tsakanin Sarakuna da masu ilimin boko.

A taron COBA na farko sai 'yan wannan qungiyar suka rabu biyu. Rukunin farko na masu ra'ayin mazan jiya ne waxanda suke so a tsaya kan ayyukan qungiyana asali; kula da makaranta, da qulla zumunci, da 'yan makaranta da sauransu. Malam A. A. Metteden ne ya jagoranci wannan vangare. Xaya vangaren kuwa wanda Malam A. A. Dogondaji ya yi wa jagora ta 'yan kawo canji ne masu son ayyukan qungiya ya wuce na makaranta ta tsunduma cikin siyasa. Daga qarshe dai sai COBA ta kauce hanya ta bi shirin da Turawa suka yi mata ta shiga harkar siyasa idanu rufe!

A wannan birgimar hankaka da qungiyar ta yi, sai ta yi watsi da batun makaranta da qarfafa ilimi ta xauki gwagwarmayar yaqi da batutuwa guda uku:

(1) a darkake Mulkin Mallaka, (2) a rusa muxlaqin mulkin Sarakuna, (3) da yaqin qwatar girma wato a kare Arewa daga danniyar 'yan Kudu.[1] To, farraqun da Turawan mulki suka shuka gashi ya fito sosai ba tare da vata lokaci ba. Da tafiya ta yi tafiya sai harkokin COBA ya koma na siyasa da adawa da Sarakuna sosai. Domin haka ne ake cewa COBA ce salsalar qungiyoyin siyasa a Nijeriya ta Arewa.[2] Don haka ne da guguwar siyasa ta qara qarfi sai 'yan Kwalejin Arewa suka cewa Sarakunansu da wa Allah Ya haxa mu ba da ku ba. Kwatsam! Sai ga harshen wutar qiyayya ya kama bal, a tsakanin Sarakuna da 'yan Boko.

A can Kudu Turawa na artabu da Siyasar Tsageranci. Amma a Arewa sun sami sauqi saboda dibarar da suka yi ta yin farraqu ta yi amfani. Turawan Mulki da suka haddasa wannan qiyayyar sai suka faqe da Sarakuna waxanda suke mulkin jama'a ta kansu. Abin takaici a maimakon 'yan COBA su darkake Mulkin Mallaka sai suka raja'a wajen darkake Sarakunansu, suka kuma hau-na-kada wajen yaqin da suka ce suna yi ne don qwatar 'yanci. Saboda haka qwayar qiyayya da Sarakuna daga makaranta aka shuka ta. Ita ce ta girma ta zama itaciya mai 'ya'ya a lokacin siyasa. Tarkon farko ya yi mummunan kamu. Har yanzu Arewa na fama da mummunan tasirinsa!

---

[1] A. M. Yakubu, *An Aristocracy in Political Crisis*, shafi na 45.

[2] *Ibid*.

A tarko na biyu kuwa wanda shi ma a cikin Arewa aka kafa shi, shi ne na xaukaka qananan qabilu mabiya addinin Kirista don su taso su ja ragamar mulkin Arewa ta hanyar ayyukan da suka jivinci ilimi kamar aikin Tsaro da koyarwa a makarantu da riqe ayyukan asibiti da sauran muhimman ayyuka. Domin waxanda ke riqe da Tsaro, da Koyarwa da Kula da lafiya su ne shugabanni, na haqiqa kuma. Wannan tarkon ma ya kama sosai. Domin a lokacin da 'yan Kwalejin Arewa ke faxa da muxlaqin mulkin Sarakuna su ke wa ilimi xaukar Sakainar Kashi, Turawa kuma sun duqufa wajen gina qananan Qabilu da ilimin boko. A bisa tsarin *Divide et Impera* sai da aka haddasa gaba tsakaninsu da Musulmi maqwabtansu. Ko da yake qananan qabilu ba su da yawa amma suna da qarfi sosai wajen ma'aikata daban-daban. A dalilin haka ne aka qirqiro sabuwar Arewa wadda ke da yawan Musulmi, amma tarin tsintsiya ne shirim ba shara. Amma ilimi da nagarta na ga Kiristocin Arewa. Su ke mulkin Arewa a fakaice ta kan ma'aikata.

Tarko na qarshe kuwa a wajen Arewa aka kafa shi. Turawan Mulki ne suka haxa Arewaci da kudancin Nijeriya don ta zama Haxaxxdiyar Tarayyar Nijeriya. Su ne kuma ya kamata su assasa abubuwan da za su haxa kan Nijeriya. A maimakon haka sai suka yi amfani da shirin *Divide and Rule* suka farraqa kan 'yan Arewa da 'yan Kudu domin su ji daxi da samun sauqin mulkin qasa. Sun gina 'yan Kudu da ilimi da tattalin arziqi. Amma saboda butulcin 'yan Kudu sai suka riqa neman korar Turawa, a gwagwarmayar qwato 'yancin qasa. A wannan lokaci sai 'yan Arewa suka nuna biyayyarsu ga Turawan Mulki. A dalilin haka ne sai suka baiwa 'yan Arewa mulkin qasa, wannan yasa Nijeriya ke tafiya a shagixe! 'Yan Kudu sai suka fahimci Turawa sun ci amanarsu. A dalilin haka sai suka xana wa 'yan Arewa karen-tsana. Bayan da aka samu 'Yancin Kai sai suka assasa gaba da hamayya da Arewa bisa dalilai guda biyu: Baraden Daular Usumaniyya sun kai farmaki Kudu har sun kai wani waje da ake kora Otta inda suka tsaya saboda qudan tsando na kashe masu dawakai. Niyyar 'Yan Jihadi su dangane da bakin teku. 'Yan Kudu sai suka lashi takobin xauko fansa ga wannan farmaki. A dalilin haka ne suka xauki garin Otta da muhimmanci da daraja. Akwai gabar maida martani ga 'yan Daular Usumaniyya. Dalilin qiyayya ta biyu kuma shi ne ganin yadda Turawan Mulki suka xauki 'yan Arewa, 'yan mowarsu. Duk da cewa 'yan Kudu ne suka fi ilimi su ne kuma suka karvi addini da xabi'un Nasara, suka yi watsi da nasu xabi'u da al'adu. Saboda haka ne bayan qarshen mulkin mallaka sai 'yan Kudu suka haxa geza da Kiristocin Arewa don su maida mummunan martani ga Daular Usumaniyya wadda Sarakuna ke wa wakilci. A dalilin haka ne suka varka kan Arewa. Suka rusa Haxaxxan Kan Arewa Kan Arewa wato *Monolithic*.

Turawan Mulki sun qware wajen farraqa kan jama'a don a ji daxin mulkinsa. Akwai varaka babba a tsakanin 'yan Kudu da 'yan Arewa. A cikin Arewa akwai varaka a tsakanin masu ilimi da ke adawa da muxlaqin mulki da Sarakunan

Arewa. Sannan kuma ana zaman doya da manja tsakanin Musulmi da Kiristocin Arewa. Kowane vangare yana neman samun fada ne a wajen Turawa. Ko da yake masu ilimi da Sarakuna suna magana da murya xaya ne akan Arewa in sun tafi Majalisar Dokoki a Ikko, amma idan suka dawo Arewa ba sa ga miciji da juna.

A cikin wannan hali ne Malam Aminu Kano ya yi amfani da jam'iyyarsa ta NEPU, ya shiga saran muxlaqin mulki, da sunan yaqin qwatar 'yancin talakawa. Amma a halin gaskiya masu ilimi 'yan boko ya yiwa yaqi. Su ne suka amfana da siyasarsa ta adawa da Sarakuna amma ba talakawa ba. Saboda haka talaka bai ci moriyar yaqin da aka ce an yi domin a qwatoshi ba, a maimakon haka ne, sai ya tsinci kansa a wani mumman hali a yanzu. An yi jifa da shi zamani kuma na watangaririya da shi saboda 'yan siyasa sun raba shi da Sarakuna sun kuma ki rungumarsa. Ai qwatar 'yanci na gaskiya da ilimi da sana'a ake yin sa, amma ba da kwarmato a bakin kasuwa ba. Wadda ta haifar da siyasar tsageranci.

An dagula Siyasar farko saboda hudowar Siyasar Tsageranci samfurin jam'iyyar NCNC a Arewa ta kan jam'iyyar NEPU. A dalilin haka ne jam'iyyar NPC da ke da goyon bayan Sarakuna da Turawa ta shiga wani karon barta da jam'iyyar NEPU wadda ke da goyon bayan Talakawa. Rikice-rikicen da ke yawan varkewa a tsakanin waxannan jam'iyyu ya haddasa wa Arewa illoli masu yawan gaske. Tun daga wancan zamani ne Arewa ta kasa samun haxxin kanta a harkar siyasa. A jihohin Gabas da Yamma kuwa suna haxa kansu su kuma tsayar da qungiya xaya wajen neman mulkin qasar nan.

Tsarin mulkin En'e shi ne tsarin da ya dace da addini da al'adun jama'ar Arewa. Saboda haka, Firimiya bai yarda a dagula wannan tsari ba. Duk da cewa 'yan Siyasa na kai wa wannan tsarin mulki suka da tokari, ba domin komai ba, sai don muxlaqin mulkin siyasa ya maye gurbin muxlaqin mulkin Sarakuna. Sardauna ya fahimci irin wannan kishi da qwanji da 'yan Siyasa ke nuna ma mulkin En'e, wato mulkin Sarakuna. A dalilin haka ne yake jaddada goyon bayansa da biyayyarsa ga wannan tsarin mulkin Arewa na asali. Alal misali, a lokacin buxe Makarantar Koyon Aikin Mulki ta Zariya, a watan Afrilu na shekarar 1954. Sardauna ya ce, "A nan Arewa muna fahari da hanyan nan tamu ta mulkin En'e. An gina ta bisa harsashi na al'ada mai qwari."[1]

Haka shi ma Malam Abubakar Tafawa Valewa, Ko da yake yana sukar muxlaqin mulkinn Sarakuna, amma yana yi ne domin a gyara wannan tsarin mulki ba don a rusa shi ba. Saboda haka, shi ne kan gaba wajen bada shawarwarin yadda za a gyara tsarin mukin En'e na Jihar Arewa. Amma sai aka gyaran ta Gyare. A qoqarin gyara shi don ya tafi da zamani sai aka dagula shi aka kuma birkita shi.

---

[1] GTK 28/4/1954.

Gyara Mulkin En'e-En'e na Jihar Arewa

Duk qoqarin da aka yi wajen tuge Tutocin Mujaddadi ya ci tura. A duk lokacin da aka jinjina Sarakuna sai aga suna nan tare da biyayyar jama'a. Saboda haka sai aka ce zai fi kyau, a yi wa tsarin mulkin En'e gyaran fuska. A wani taron tsohuwar Majalisar Wakilan Arewa, M. Abubakar Tafawa Valewa ya kawo shawara a duba tsarin mulkin En'e-En'e na Jihar Arewa, a gyara shi, yadda zai yi dai-dai da ci gaban da zamani ya kawo. Wakilan cikin majalisar duka suka goyi bayansa. Daga nan gwamnati ta sa Mr. D.A. Pott, Di'o na Kano, da Mr. K.P. Maddocks, Di'on qasar Kuza, suka yi rangadi mai yawa a Jihar Arewa, suka jiwo ra'ayin jama'a, sa'an nan suka tsara abubuwan da suka tara, suka miqa wa gwamnati. gwamnati kuma ta miqa wa Zavavvun Mashawartan da aka zavo daga Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilan Jama'a, domin su bi cikinsa, su shawarta abin da suka ga ya kyautu a yi, game da gyaran mulkin En'e-En'e. Zavavvun Mashawartan nan, su ashirin da bakwai (27) ne Mr. A.J. Knott, wakilin Sakataren Jihar Arewa, shi ne na cikon ashirin da takwas (28), kuma shi ya shugabanci taron da suka yi. A cikin Zavavvun Mashawartan, akwai Mr. C.R. Niven, Razdan na qasar Kuza; Mr. K.P. Maddocks; Mr. D.S. Stephens, wakilin babban lauyan gwamnati; Sarkin Musulmi Sir Abubakar; Shehun Barno Umar Ibn Muhammad; Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayaro; Sarkin Bauci Yakubu; Lamixon Adamawa Ahamadu; Sarkin Katsina Alhaji Sir Usuman Nagogo; Sarkin Zazzau M. Ja'afaru; Etsu Nupe Muhammadu Ndayako; Sarkin Ilorin Abdulqadiri; Atta na Igbirra Alhaji Ibrahima; Sarkin Kafi Ahmadu; Sarkin Jema'a Muhammadu; Walin Barno Muhammadu; Sardaunan Sakkwato Ahmadu; Ma'ajin Adamawa Muhammadu Ribaxu; Makaman Bida Aliyu; M. Abubakar Tafawa Valewa; Ciroman Kano Alhaji Muhammadu Sanusi; M. Yahaya Ilorin; Sarkin Birom Rwang Pam; Sarkin Gabas Iro Katsina; Ma'ajin Zazzau Sanusi; Sarkin Loko Umaru da Alhaji Saidu Adejo.

Waxannan Zavavvn Mashawarta, sun yi taro a ranar 20 da 21 ga Yuli, 1951. Sun sake yi a ranar 7, da 8, da 9 ga Agustan shekarar 1951, sa'an nan suka sa hannu, suka gabatar da wannan labari, game da kyautata sha'anin mulkin En'e-En'e.sun ba gwamnati shawara a bisa waxannan batutuwa:

En'e-En'e da Majalisu

Kwamitin nan sun duba dukkan yadda aka kafa Majalisun qauyuka, da Majalisun Gundumomi, da na shawarwarin Ra'ayin Jama'a, da kuma Majalisun En'e-En'e. Sun ko yarda, wannan hanyar, ita ce hanya mafi kyau, ga yadda za a fi samun jama'a su so sa bakunansu cikin sha'anin mulkinsu, da ayyukan qasarsu. Irin waxannan majalisu, lallai ne En'e-En'e su tabbatar da su sosai. To, amma duk da haka, ba za a ci amfaninsu ba, sai am bai wa ko waccensu waxansu kafaffun ayyuka da suka sani. Sabo da haka aka ga ya wajaba a bayyana irin shirin ko

wacce, da kuma irin ayyukanta. An lura, ba zai yiwu a kawo shawarwarin da za su dace cif da dukan En'e-En'e ba, waxanda ke da tushen hanyoyin mulki daban-daban, da kuma mabambantan matsai wajen qware wa ga ko wace En'e. Amma an yi tsammani waxannan hanyoyi na manufar ayyukan nan, za su yi taimako wajen bayyana halayen da za a bi da ingancin nan.

A waxansu halaye, inda waxansu En'e-En'e ke tarayya a cikin Baitul-maili guda, akwai buqata zahira ga kafa qwaqqwaran mulkin igiyan nan da ta haxe duka En'e-En'e nan baki xaya, da kuma kwamiti mai zatar da sha'anin mulkin nan. Amma an ga wuraren nan suna buqatar a duba halayensu, xaya-xaya, don haka ba zai wadatar ba, a jimillata bayani kan irin abubuwan nan baki xaya. Kwamitin nan na ba da sawarar ya kamata a kafa wa ko wace majalisa xakin shawara, wand zai yi dai-dai da ita.

Shirin Majalisun Qauyuka

Kwamitin nan na ba da shawarwari ya kamata duka maza, baligai, masu biyan haraji, da waxanda doka ta yafe musu biyan harajin, waxanda ke zaune a gidajensu dafa'an a cikin yankin qauyen nan, su zavi wakilan da za su shiga Majalisar qauye, zuwa matsayin shekara uku. Bayan ko wace shekara, sulusin wakilan nan za su riqa fita, ana sake zave. Amma kuma su wakilan nan da suka fita bayan shekara guda, in an so, ana iya sake zavensu, su ci gaba.

Yawan wakilan wannan majalisa, En'en nan ce za ta yanke. Su wakilan nan da jama'a suka zava, su kuma za su zazzavo waxansu qayyadaddun wakilai, waxanda za su qara cikinsu, saboda su isam ma waxansu mabambantan halaye na wata qungiya musamman. Irin waxannan wakilai da aka qara, tsawon lokacinsu shekara guda ne kurum.

Ayyukan Majalisun Qauyuka

Su waxannan majalisu, za su riqa ba da shawara ga Majalisar Gunduma, kan waxansu babubuwa, kamar naxa masu unguwanni, da rabon haraji, da kuma abubuwan da suka shafi ci gaban qauyensu. Su duba kuma sha'anin Odoji na En'e, da duk irin abubuwan da Majalisar Gunduma ta turo musu.

Dagaci, shi ne zai shugabanci taron nan a ko yaushe, muddin yana sarautar dagacin. Shi ne mai shirya yin taron, wanda za a riqa yi aqalla sau xaya, ko fiye da haka, in ana buqata, bayan ko wane wata uku. Malamin dagacin, shi zai zama sakataren majalisar. Za a kuwa riqa aikawa da kofen labarin abin da aka yi a ko wane taro zuwa ga hakimi.[1]

A wajen shirin Majalisun Gundumomi, kwamiti na ba da shawarwari cewa 'yam Majalisun Gundumomi, Majalisun qauyuka ne za su riqa zavensu, bayan ko wace shekara, daga tsakaninsu. Amma kuma ana iya sake zavensu, bayan ko wace

[1] GTK, 20/2/1952, shafi na 10

shekara, daga tsakaninsu. Amma kuma ana iya sake zaven waxanda suka fita bayan shekaran nan, su sake cin gaba. Yawan wakilan da za su zo daga ko wane qauye, zai zama gwargwadon yawan mazajen qauyen nan ne, baligai, yadda En'e ta tsara. Dukan Dagatai za su kasance cikin majalisan nan, muddin suna cikin sarautarsu. Kuma a cikin Majalisun Gundumomi, kamar yadda aka yi a cikin Majalisun qauyuka, za a zavo waxansu mashawarta a qara, saboda su isam ma waxansu mabambantan halaye. Hakimi shi ne shugaba ko yaushe, muddin yana cikin sarautar hakincin.

Ayyukan Majalisun Gundumomi

Majalisum Gundumomin nan, babban aikinsu, shi ne kula da kashe kuxaxen Majalisun Gundumomin. Suna kuma iya xaukar waxansu takalifai na kuxi da En'e za ta riqa fawwala musu lokaci-lokaci. Kwamitin nan ta yi maraba da jin a cikin sabon Littafin Ayyukan Baitul-maili *Financial Memoranda*, wanda a ke shiryawa a yanzu, za a ajiye waxansu qa'idodi na yadda za a riqa fawwala wa Majalisun Gundumomi waxansu iko na kuxi. An yarda, a inda duk aka sami waxansu Majalisun Gundumomin da suka nuna gwaninta da amincewa, game da kuxin nan na Majalisun Gundumomi da aka keve musu, to, ko wace shekara sai a bai wa irin waxannan majalisun hanyar shirya istimat na kuxin kashewarsu na shekara, ga gundumomin da su ke wakilta, cikin iyakacin rabon kuxin da aka yanka musu, don En'e ta ba su iznin kashewa. Kuma a inda aka dace, sun ba da shawarwari, don samo hanyoyin qara kuxinsu, ko ta qara haraji, ko ta wata hanya, saboda a sami biyan ko wane irin qarin aiki na kashe kuxin nan, da suka kawo shawarwari a yi musu, wanda ya shige qarfin rabon kuxin da su ke da shi.

Da farko, za a kwatanta yawan abin da za a xebe, saboda tsare ayyukan En'en nan, waxanda su ke na jama'ar qasa ne duka baki xaya. Sa'an nan a xebe waxannan kuxi. Bayan haka, sauran su ne ragowar waxanda za a kashe kan istimat. An dai yarda, duka, ba dukan waxannan majalisu za a iya ba wannan izni ba gaba xaya, saboda bambancin matsayin gwanintarsu da saninsu. Kuma tafiyar da harkokin ma'aikatan En'e, da xaukarsu aiki, da tarbiyyarsu, da sallamarsu, duk a bar su ga En'e ta qasan nan duka. Albashin irin waxannan ma'aikata, za a biya su ne daga cikin kuxin nan da aka ware wa Majalisun Gundumomin nan.

Ban da waxannan takalifai na kuxi, kuma Majalisun Gundumomi za su duba duka shawarwarin da Majalisun qauyuka suka turo musu, za su kuma ba da shawara ga En'e bisa naxa Dagatai. Za su yi shawara kan ko waxanne irin ayyuka na raya qasa a cikin gundumomin nan nasu, da kuma kan qa'idodi da Odoji na En'e, su aika da shawarwarin nan nasu ga En'e. Za su yi shawara kan naxa masu unguwanni, bayan sun duba shawarwari Majalisun qauyuka, sa'an nan su tabbatar. Za su riqa yin taron nan nasu a qalla sau xaya, ko fiye da haka in ana buqata, bayan ko wane wata uku. Malamin hakimi, shi zai zama sakatare, mai rubuta

labarin ko wane taro. Hakimi da ke shugaba, zai riqa shirya yin wannan taro, kuma ya ga an aika da kofe na labarin taron nan da aka yi, zuwa ga En'e.[1]

Kwamitin nan ta lura, a cikin manyan birane, al'amuran mulkin hukuma sun bambanta ainun, kuma sun fi cuxewa, fiye da na qauyuka. Amma duk da haka, an ga ana iya sa Majalisun Biranen nan, su kuwa dace, cikin tsarin ayyukan nan na Majalisun qauyuka da Majalisun Gundumomi, waxanda aka riga aka yi bayaninsu a can farko. Yawancin hedkwatocin birane na En'e, da ma tuni ana xaukarsu kamar gundumomi ne. Majalisun Biranen nasu, don haka, sai a xauke su kamar Majalisun Gundumomi. Daga nan za su riqa aikawa da wakilansu zuwa ga Majalisun Shawarwari Ra'ayin Jama'a. Manufan nan ta dai-daita iyakar qasar Majalisun qauyuka da yawan wakilan da za su tura ga Majalisun Gundumomi, gwargwadon yawan mutanensu, za ta tabbatar da cewa za a kula sosai da buqatun manyan garuruwan da ke cikin qasar gunduman nan a cikin Majalisun Gundumomi, da na Shawarwari Ra'ayin Jama'a. Don haka, zaven wakilan nan, da shirinsu, da hanyoyin aikiinsu, za su zama dai-dai kamar na Majalisun qauyuka, ko na Majalisun Gundumomi ne. "Kwamitin nan kuma ta ba da shawarwari lallai ya kamata a duba dangantakar da ke tsakanin garuruwan da ke hannun Kantoma da En'e-En'e.

Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'a

Kwamiti ta duba bayanin da ya bayar, game da kafawar Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'ar Sakkwato, da shirinta, da irin aikinta. An dai yarda duka, irin waxannan Majalisun Shawarwari Ra'ayin Jama', ba shakka su ne manyan tubalan ginin mulkin hukumar qasa. Babban amfaninsu, shi ne suna ba da damar En'e ta sami haxuwa da jama'ar birni da qauye.

Shirin Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'a

Kwamiti ta yarda, masu shiga wannan Majalisa ta Shawarwari Ra'ayin Jama', Majalisun Gundumomi ne za su zavo su daga cikinsu, amma En'e kuma na iya qara waxansu Zavavvun Wakilanta, don su tabbata cikin majalisan nan, ko kuma don waxansu taro musamman, waxanda a ganinta lallai sun kyautu su zama cikin majalisan nan. 'yan Majalisar En'e duka za su shiga, bisa matsayin aikinsu. A waxansu halaye kuma, har shugabannin ayyuka ma ana iya sa su cikin majalisan nan, su zama Tabbatattun Mashawarta, ko kuma saboda waxansu taro musamman. Shugaban taron, En'e ce za ta naxa shi, shi ne zai riqa shirya kiran ko wane taro na majalisan nan.

[1] GTK, 27/2/1952, shafi na 10

Ko wane irin zave da waxansu jama'a suka yi, da kuma na waxanda aka qara, tsawonsa shekara guda ne kurum, amma kuma ana iya sake zaven mashawartan nan, ko wakilan, su sake cin gaba, bayan qarewar shekaran nan.

Ayyukan Majalisun Ra'ayin Jama'a

Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'a za ta duba maganganun da suka fito daga Majalisum Gundumomi, da kuma ko wace magana da En'e ta tura mata. Za ta duba, kuma ta faxi ra'ayinta kan duka qa'idodi da Odoji waxanda En'e ke nufin kafawa. Kuma, a inda ta roqe su musamman, za su duba ko wace irin doka da gwamnati ke nufin kafawa, wadda ta shafi jama' sosai da sosai. Za su duba istimat na En'e, na kuxin shiga da na kashewa, a ko wace shekara, su kuma kawo shawarwari tsare-tsaren yadda za a inganta qasar En'en nan baki xaya. Duka shawarwarin da Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'a ta qulla, za a aika da su ga En'e ne.

Ya yarda zai shirya aikawa da cikakken bayani na wannan majalisa, don ya taimaki En'e-En'e wajen kafa waxannan majalisu da sauri.[1]

Kwamitin nan ta duba maganar dangantaka tsakanin Sarakuna da majalisunsu, filla-filla. A cikin taron, an fahinta tun kafin zuwan Turawa ma, ikon Sarki na gargajiya a nan Arewa yana yinsa ne bisa shawarwari, da kuma taimakon mashawartansa na gado. Bayan zuwan Turawa, ga alama, sai gwamnati ta fuskanci mai da qarfin ikon komawa ga Sarki. Misali, ko a wurin naxa Sarki, bisa ga Dokar En'e, sai aka sa Sarakuna su kaxai, da ba da ambatar majalisa ba. To, a kwana a tashi, qarin nauyi, da wuyatar aiki na zamani, sun tsananta wa Sarakuna buqatar shawarwari majalisunsu da taimakonsu. Har ma gwamnati ta shaidad da haka, wajen tabbatar da zaven 'yam majalisun Sarakuna. Muhimmiyar shaidan nan, ita ce hanyar nan ta majalisu da aka bi wajen zaven Wakilan Jihar Arewa, a lokacin fitowar Sabon Shirin Mulki a shekarar 1946. Kwamitin nan tana lura da cewa naxa 'Sarki cikin majalisa' ya zama En'e, bisa ga Dokar En'e, ko kaxan ba zai kau da girmansa na gargajiya ba, bisa shi ne shugaban addinin qasan nan tasa. To, amma ta yarda, a duka abubuwan da ke shafar tafiyar da mulki tsantsa, kamar su yin qa'idodi, da naxawa ko sallamar 'yan Majalisar En'e, da ma'aikatan En'e, manya da qanana, Sarki ya saba da neman shawatar majalisarsa. Don haka, ko bisa ga al'ada, da kuma hanyar da aka saba bi a yanzu, dangantakar Sarki da majalisa tasa, za a fi bayyana ta sosai, idan aka ambaci 'Sarki cikin majalisa', wato, *Chief-in-Council*, fiye da a riqa kiran 'Sarki shi kaxai', wato *Sole Native Authority*, yadda a ke yi yanzu.

Am ba da shawara, 'Sarki cikin majalisa', ko da yake a harshen turanci yana da cikakkiyar ma'ana bisa fuskar doka, duk da haka sabon abu ne a cikin Hausa. Don

[1] GTK, 5/3/1952 shafi na 10

haka lallai ana buqatar, qila ta yin gyara ga Dokar En'e, a ba da cikakken bayanin kalamin nan, 'Sarki cikin majalisa', yadda ma'anarsa ta ke ga doka, don sawwaqe wannan matsala. Wannan bayani zai nuna Sarki yana iya sava wa shawarwari majalisa tasa, kamar yadda Gwamna yake da tasa majalisar. Amma, in ya yi haka, lallai ya rubuta ya shaida wa Razdan dalilin savawan nan tasa.

In Sarki ya qi Xaukar Shawara ta Majalisa da ta Razdan fa?

Idan Razdan ya ga Sarkin nan ya yi kuskure, da ya sava shawarwari majalisarsa, zai sanad da Sarkin nan haka. Idan Sarki ya qi kula da shawaran nan da Razdan ya ba shi, Razdan zai ba da labarin wannan magana duk ga Leftana Gwamna a cikin majalisarsa, don shi ya yanke magana. Idan kuma Razdan ya ga wata shawara da Sarki ya yi tare da shawarwari majalisa tasa, ga alama za ta soki zaman lafiyar qasa, ko oda, ko kyakkyawan mulki na qasan nan, yana iya umurta a jingine aiki da shawaran nan, har sai an ji abin da Leftana Gwamna a majalisa zai yanke. Nan da nan Razdan zai ba da labarin maganar ga Leftana Gwamna a majalisa, don ya yanke.

Sarki Cikin Majalisa

Bisa wannan nufi, da kuma waxannan dalilai, kwamiti ta yarda a sa waxannan kalmomi, 'Sarki cikin majalisa', maimakon 'Sarki' kurum, a cikin Babin Naxa Sarakuna a Dokar En'e. Sabo da haka, am ba da shawarwari a inda duka aka ambaci Sarki, a bisa 'Sarki shi kaxai' ya kamata Sarakuna su yarda a gyara wannan lafazi.

Game da shiga majalisun En'en nan, kwamiti na ba da shawara, bisa ga matsanantan buqatun raya qauyuka, ya kamata ko wace En'e ta aza wa Xan-majalisa guda musamman alhakkin wannan babban aiki na raya qauyuka. Babban aikinsa na farko, shi ne ya tabbatar da duk ayyukan da aka yarda da yinsu, am fara su, bi da bi, gwargwadon muhimmancinsu, don a hana gunaguni game da jin yinsu.[1]

Kwamitin nan ta saurari labarin ayyukan Kwamitin Hukumar qasa, da amfaninsu, wanda suka yi sa'ar ji daga Mr. R.S. Hudson, Shugaban reshen da ke riqe da al'amuran Afirka, a ofishin sakatare mai kula da Qasashen da ke Qarqashin mulkin Ingila. Ta kuwa ya sha'awar labarin nan. Kwamitin nan, musamman, ta lura da shawarwari da Mr. Hudson ya bayar, game da yadda za a shirya irin waxannan kwamiti-kwamiti, masu lura da sha'anin ma'aikatun hukuma daban-daban, su yi aiki tare da Majalisun En'e, da na Shawarwari Ra'ayin Jama'a. Shugaban ko wace kwamiti, zai kasance xam majalisar da ke lura da harkar wannan aiki ne, a cikin majalisa. Kwamitin nan, ita ke da ikon gudanar da

[1] GTK, 12/3/1952 shafi na 10

ayyukan sha'anin mulkin nan na yau da kullum, amma duka wata babbar magana, kamar su kafa Odoji, da qananan qa'idodi, ko kafa hanyoyin samun qarin kuxi ga qasa, waxannan sai an kai su gaban Majalisar Shawarwari Ra'ayin Jama'a, kafin a aike da su ga En'e ta tabbatar.

Kwamiti ta lura, wannan hanya ta mulkin hukumar qasa da aka nuna, game da naxa kwamiti daban-daban, za ta yi taimako ainun ga sabar wa jama'a yadda a ke gudanar da al'amuran mulkin hukuma. Ta nan kuwa kowa zai gane irin alhakkinsa game da ayyukan nan, tun daga kan ma'aikatan En'en nan, su kansu, har zuwa kan dukan sauran jama'ar da ke sha'awa cikin sha'anin mulkin hukuman nan ta qasa. Amma kuma an sami shakka a nan, ko jama'a za su yarda su yi aiki a kwamitin nan, ba tare da samun wani lada ba, sai kurum a mayam musu da kuxin sufurin da suka kashe? An ga a ce jama'a su kasa yin aikin taimakon 'yanuwansu, wai sai da lada, wannan zai rusa duka shirin nan na nufin haxa jama'a da sha'anin mulkin qasarsu.

Kwamitin nan ta yi maraba da labarin da shugaba ya bayar, cewa za a qara fawwala wa En'e-En'e waxansu iko game da kuxi, wanda a ke nufin a sa cikin sabon Littafin Ayyukan Baitil-mali, da a ke sakewa. Hanyoyin fawwala ikon kuxin nan da a ke nufin kafawa, suna nuna muddin an tsare waxansu sharuxa, game da tsArewar qayyadadden kashi na kuxin da za a keve, tsakanin kuxin kashewan nan, istimat xin nan na En'e na shekara shekara, bisa qa'ida, Chief Commissioner zai yarda da shi, ba da wata sakiya ba. Har yau kuma, za a bai wa En'e waxansu ikon yarda da qarin kashe kuxi, da kuma ba da rance.

Kamar yadda aka ba da labari a babin Majalisun Gundumomi, kwamiti ta duba zancen qara fawwala wa Majalisun Gundumomi ikon kashe kuxi, inda su majalisun nan suka nuna za su iya yin amfani da qarin ikon nan, in En'e ta yardam musu.

Qa'idodin Aiki Da Na Tarbiyyar Ma'aikata

Kwamitin nan ta ji, ta kuma yarda, kwatancin Qa'idodin Aikin Ma'aikatan En'en nan da aka shirya a cikin shekarar 1947, aka aika da su ga duka En'e-En'e, don a sami ra'ayinsu a kai, nan gaba kaxan za a sake buga su a sabon xaba'i, saboda ra'ayoyin nan da aka tattara, da kuma canje-canje iri-iri da aka yi, aka tabbatar, game da Qa'idodin Aikin Ma'aikatan gwamnati. An yarda, ko da yake lokaci bai yi ba, da za a iya yin haxaxxun qa'idodi, waxanda dukan En'e-En'e na Arewa za su xauka gaba xaya, ba tare da samun wani savani ba, kuma ko wace En'e a yanzu tana iya yin dokoki na ma'aikatanta, duk da haka, an ga lallai ana buqatar abubuwa su zama bai xaya, ko ina a cikin Jihar nan. Don haka, an yarda a kafa kwamiti ta mutum 12, ko wane wakili ya wakilci En'e-En'e na lardinsu, su haxu nan da nan, don su gama bin sabbin Qa'idodin Aikin Ma'aikatan En'en nan, sa'an nan a aika da su ga ko wace En'e, don kafawa a qasashenta.

Kwamitin nan ta roqi a aika wa En'e-En'e duka kofen sake-saken da a ke son yi a shirin nan na farko, ba tare da wani jin ba, don a tabbatar da cewa En'en nan za su sami damar tabbatar wa wakilan nasu 12, da ke cikin kwamitin nan, ra'ayinsu da za su zo tare da shi, tun kafin su taru. An kuma yarda su kwamitin nan na duba Qa'idodin Aikin Ma'aikatan En'e su riqa haxuwa a kai a kai, misalin bayan ko wane wata uku, don su duba ko wace sakiyar da za ta zama wajibi a I lokaci-lokaci.

Binciken Hanyar Tarbiyya

Kwamitin nan na bada shawarwari ya kamata a yi bincike na haqiqar irin damar da ke samuwa, da kuma irin abubuwan da za a koyar, don tarbiyyar ma'akatan En'e, waxanda ke ayyukan ofis, da na harkokin mulki ga En'e nan, har da 'yam majalisu, da Hakimai, da Dagatai, domin a iya tabbatar da ana ba da isasshiyar kula ga matsananciyar buqatan nan, game da haqiqar kyautatuwar sha'anin nan, bisa wannan hanya. Bayan wannan, sai kuma a naxa wata qaramar kwamiti, don ta ba da shawarwarin da za a bi.[1]

Kwamitin nan ta yi doguwar shawara kan dangantakar Turawan mulki da En'e-En'e. Am fahinta, babban aikin Turawan mulki, shi ne su zama bakin gwamnati, ga bayyana nufinta. To, amma kuma, bisa wakilan Gwamna a cikin qasa, zartaccen aikinsu, shi ne lallai su tabbatar da tsArewar zaman lafiyar jama'a, da kyakkyawan mulki ga dukan al'amura. Dokar En'e, da Dokar xakunan shari'a, da waxansu dokoki 'yanuwansu, sun danqa wa Turawan mulki waxansu yardaddun iko da ayyuka. Baicin waxannan ikon na doka, ba su da waxansu ayyuka, illa na ba da shawara ga En'e-En'e na lardin da aka liqa su gare shi, sai fa ko ga qasashen En'en da ci gabansu bai isa su iya yin ayyukansu ba, ba tare da taimako ba. Waxansu mashawarta sun bayyana cewa a cikin shekarun nan, waxansu daga cikin Turawan mulki fa sun wuce aikinsu na ba da shawara ga En'e-En'e, sun karve ragamar mulkin En'e, sun mayar ga kansu. An yarda cewa wani lokaci, in akwai kasawa, da rashin kula, da mugun hali ga ma'aikatan En'e, manyansu ko qananansu, wannan dai-dai ne ga Turawan mulki su shiga su da kansu. In sun yi haka kuwa, lallai ne su ba da labari a gaba. To, amma duk da haka dai, an ga ya fi kyau a ci gaba da yadda aka saba kamar da, wato En'e ko wakilanta, su riqa yin ayyukan nan da kansu.

[1] GTK, 19/3/1952 shafi na 10

Rashawa da Zalunci

Kwamiti ta duba zance amsar rashawa da zalunci na masu aiki, waxanda suka yawaita ko ina, ta kowace hanya. An yarda, bisa hangawar da aka yi, hanyar kurum da za a iya kau da wannan mugun abu, ita ce ta fuskar matsawar jama'a su da kansu.

Kwamiti ta ga aikin En'e ne, musamman, da ma'aikatansu, su tashi tsaye sosai, cikin martabar da su ke da ita ga jama'a, su waye kan jama'a a cikin wannan harka, kuma su da kansu in an kawo musu masu wannan laifi, su jimqe su sosai, yadda suka cancanta, ba sani ba sabo. Yin sako-sako a cikin wannan tarnaqaqqen aiki, mai kawo baqin jini, shi ne fa zai jawo shigar Turawan mulki dole a cikin zarafin. Abin kuwa da aka nuna ba a cika so ba ke nan, a cikin shawaran nan ta dangantakar Turawan nan da En'e-En'e.

Ma'aikata Mataimakan Jama'a ne

Har yau kuma, an qarfafa cewa Majalisun Gundumomi, ban da babban aikin nasu na raya qauyuka, za su iya, kuma ya kamata, su yi amfani qwarai wajen waye kan jama'a, game da karvar rashawa da zalunci na masu aikin En'e da gwamnati. Muddin dai su wakilan waxannan majalisu jama'a ne suka zave su da kansu, kuma an sakam musu ragamar gudanar da mulkinsu na yau da kullum, to, lallai ne su ba jama'a filin 'Faxi Sonka', inda za su riqa kawo qararrakinsu, game da irin waxannan al'adu, nan da nan, don neman magani.

Da jama'a da ma'aikata, duka lallai ya kamata a nuna musu, su haqqaqe su ma'aikatan nan fa, manyansu da qanananansu, duka mataimakan jama'a ne, don kuwa suna samun ladansu daga cikin harajin da jama'a suka biya ne. Don haka kuwa, ashe ba su da wata hujja ta bixar kyauta, ko wace iri, daga hannun jama'a, don yin ayyukan da a ke biyansu albashi saboda su. Kwamitin nan kuma ta lura cewa sau da yawa rashin bin odar jama'a, shi ne ke ba ma'aikatan nan damar faxawa cikin wannan muguwar hanya.

Kyauta ta Al'ada

Kwamiti na ba da shawara cewa ana buqatar a shirya yadda za a iya bincika irin kyautan nan ta al'ada, da a ke yi tsakanin Sarakuna, da Hakimai, ko Dagatai, da jama'arsu, don a iya gane bambancinta da rashawa ko zalunci. Wannan bincike fa, ya yiwu ya kai har ga sake duba albashinsu irin mutanen da fa su ke riqe da waxannan matsayai.

Kwamitin nan ta ga lallai ya kamata a duba Dokar En'e, da duka dokokin da ke shafar En'e, filla-filla. A kuwa duba su da kyau, don a dai-daita su da hanyoyin

nan, da kuma manufan nan, da aka ba da shawarwari kafawa a cikin wannan labari. [1]

Tsarin Mulkin En'e da ya yi fiye da shekaru xari kafin zuwan Turawa sai ya yi kicivis da mulkin mallaka. Arewa lokacin kuwa Turawan Mulki da'yan bokon wannan zamani suka haxu suka yi masa sakiyar dababu ruwa. A maimakon su gyara mulkin En'e sai aka lalata shi. An rikirkita Sarakuna a kan bin jagorancin Sarkin Musulmi Bello da Shehu Mugili, a dalilin haka ne sai aka yaudare su suka saki reshe suka kama ganye. Gyare-gyaren mulkin En'e sai ya vata shi. Turawan mulki da 'yan bokon wannan zamani masu hamayya da gaba da mulkin En'e ne. Saboda haka babu yadda za su yi masa gyara mai inganci. Domin ingancinsa zai zama barazana ga 'yan boko masu jiran gadon mulki, in 'yanci rani sun koma gida a shekarar 1960. Kamar yadda aka yaudari Sarakuna, aka hana musu Kyautar Al'ada, haka kuma aka sake yaudararsu dacewar muxlaqin mulkinsu wato *Sole Native Authority* haramun ne, saboda haka sai su rusa shi da kansu.

Illar mulkin Dimukuraxiyya mafi mini shi ne raba mutane da xabi'u da al'adunsu a hankali da sunan 'yanci da ci gaba. A kullum neman ra'ayin jama'a masu yawa ake buqata wajen zartar da doka amma ba mutane masu ilimi da hankali ba. A wannan shiri sai aka wargaza mulkin 'yan En'e da aka cusa masa siyasa da sunan Dimukuraxiyya don ya tafi da zamani. A rubucewaxannan tsare-tsare da aka yi wa mulkin En'e suna bayar da sha'awa. Amma aiwatar da su shi ne jihadi.

Tun da an shimfixa tsarin Siyasa a mulkin En'e sai aka numfasa kan muxlaqin mulkin Sarakuna da ya ja shekara da shekaru yana tsole wa 'yan Siyasa idanu. Babbar matsalar mulkin Sarakuna da 'yan Siyasa ke kuka da shi, shi ne muxlaqin mulki. Saboda haka, sai Sir Abubakar ya yi wa wannan matsalar karan tsaye. Saiya shiga sarar reshen da masarautar Arewa ke tsaye a kai, wato *Sole Native Authority*.

Sarkin Musulmi ya Soke Muxlaqin Mulki

A ran 25 ga Fabrairu 1952, Majalisar Sarakuna ta yi taronta na duba istimat a *Lugard Hall*. A wannan taro ne ta duba matsayin Sarakunan Jihar Arewa dukkansu, musamman saboda la'akari da cece-ku-cen da 'yan siyasa ke yi akan muxlaqin mulkinsu. A wannan lokaci mulkinsu na shan yawan suka da tokari daga 'yan Siyasa waxanda ke ta qorafin wai Sarakuna basa aiki, basa kuma shawara da majalisunsu a harkokin mulkinsu na *Wahadahu La Sharika Lahu*! A dalilin haka ne sai Sarkin Musulmi Sir Abubakar ya yi kira ga duk Sarakuna da su riqa aiki tare da shawara da taimakon majalisunsu. Ya ce:

[1] GTK , 26/3/1952 shafi na 10

Majalisan nan ta Sarakuna ta gani, kuma ta gane, a ainihin gaskiya, irin ikon da Sarakuna su ke da shi, a bisa al'ada a nan Jihar Arewa, da ma can suna tafiyar da ma'amalolin mulkinsu ne tare da shawara da taimakon majalisunsu. Saboda haka, wannan majalisa ta ga ya kamata kowane Sarki na Jihar Arewa, wanda yake shi kaxai ne ke da iznin zartarda kowane abu (Sole Native Authority) sai ya koma matsayin Sarki cikin majalisa, wato Native Authority-in-Council. Dukkan shirye-shiryen dokokin da za su daidaita wannan sai a gabatar da su.[1]

Sarkin Musulmi Sir Abubakar ya kare majalisar Sarakuna ne daga zargin da ake yi kan muxlakin mulki. Duk da cewa akwai alamun qazafi babba a wannan zargi. Saboda haka ne ya ce tun fil azil kowane Sarki na buqatar ya tafiyar da harkokin jama'arsa ne ta aiki tare da shawara da majalisara. Ba shi cikin tsarin mulki, Sarki ya riqe komai a hannunsa shi kaxai wato *Sole Native Authority*. Don haka doka bata lamunce da haka ba duk mai mulkin *Wahadahu La Sharika Lahu*, to, an buqace shi da ya koma matsayin Sarki-Cikin-Majalisa wato *Native Authority-in-Council* wanda shi ne tsarin mulki na asali a Jihar Arewa. Amma wannan sabon Sarki Cikin Majalisa yana da mummunar manufa. Saboda shiri da ya maida Sarki kamar kowane xan Majalisa ba shi iya zartar da komai sai inda ra'ayin jama'a masu yawa suka rinjaya.

Duk da haka Majalisar Sarakuna ta goyi bayan wannan shawarwari. Domin a da can Sarakuna basa zartar da hukunci sai da shawarwari majalisaru. Amma saboda illar *Indirect Rule* sai Sarakuna suka karkata wajen shawara da Razdan kawai, a dalilin haka sai suka zama masu cikakken ikon. A wannan dagulallen tsari sai Sarakuna suka koma farantawa Razdan rai amma ba jama'arsu ba, har ma 'Yan Majalisunsu suka zama gani-nayi-ka kawai wato sai aka maida su hannun rediyo. A dalilin haka ne sai wasu Sarakuna suka ga ya fiye musu su yi suna wajen nuna ikon yin komai su kaxai, Ko majalisarsu na so ko bata so. Idan majalisa ta ba su shawara kuma sai sun ga dama za su xauki shawarwari. Illar *Indirect Indirect Rule* ce ta haifar da wannan matsala. Razdan *Ummul Haba'isin* muxlaqin mulkin da ake cece-kuce a kansa. Razdan ko Di'o ne da laifin wannan irin mulki da ya dagula al''amuran mulki baki xaya. Wannan hali sai ya kaucewa tsarin mulkin Sarakuna na asali. Saboda haka sai Sarkin Musulmi ya tsawatar, ya kuma soke wannan iko na *Sole Native Authority*, ya kuma yi kira ga waxannan Sarakuna da su riqa aiki tare da 'yan majalisarsu wato mutum guda ya dai na zartarwa ko ya hana zartar da komai shi kaxai ba tare da amincewar 'yan majalisarsa ba. To, idan Sarki ya bi wannan umurni sai Razdan da Di'o su zarge

[1] GTK Ta 495, 5/3/1952

shi da laifin rashin bin tsarin mulki yardajje wanda komai za a yi sai da shawara da amincewar Razdan ko Di'o amma ba majalisar Sarki ba.

Tsarin mulkin Sarakuna duk da illolin Mulkin Mallaka da ke dagule shi yana tafiya dai-dai da zamani saboda an kafa shi ne akan qwararan shika-shikan mulki tabbatattu waxanda suka samo asali daga Shehu Mujaddadi da xansa Bello, da qanansa Shehu Abdullahi Gwandu da kuma Shehu Magil. Haka kuma wannan tsari bai lamuncewa cin hanci da rashawa ba ko kaxan. A dalilin haka ne ma Sarkin Gwandu Yahaya ya mike a gaban Majalisa, ya roqi Sarakuna dukkansu da su taimaka, a tasam ma wani sabon qoqari game da yaqi da rashawa da toshiyar baki. Ya kawo shawara, "majalisan nan bayan ta yarda lallai akwai rashawa da toshiyar baki a cikin kowace ma'amala ta jama'a, ta ga ya kamata Sarakuna da shugabanni su yi kowane irin qoqari su gano masu yin wannan laifi, su hore su, ba da wani zave ba."[1] Majalisar Sarakuna kuma ta goyi bayansa.

Kamar yadda aka yi bayani ne Sarkin Gwandu Sir Yahaya ne wanda ya fara kira da faxa da rashawa da cin hanci a zamanin mulkin shi. Saboda haka duk da zargi da tokarin da 'yan Siyasa kewa Sarakuna, sune kan gaba wajen yaqi da rashawa da toshiyar baki a tarihin Jihar Arewa. Duk abubuwan da Sarakuna suka yi masu kyau babu mai ce masu son barka a saboda neman yadda za a yi a tuge mulkinsu ake yi ba yadda za a yi a havvaka amfana da shi ba.

Duk qorafin da masu ilimin zamani ke yi shi ne Sarakuna sun kankame komai basa shawara da kowa. Wato sun handama da babakere. Saboda haka ne suke fafitikar kafa tsarin Sarki Cikin-Majalisa ba domin komai ba sai don su sami damar yi wa Sarki taron dangi a Majalisa da hurumin Siyasa. A dalilin haka ne Mai Wandon Qarfe yake qara jaddada ayyukan Sarkin Musulmi Sir Abubakar a qoqarinsa na gyara tsarin mulkin Sarakuna. Saboda haka ne yake kira ga Sarakuna su riqa xaukar shawarwari 'yan Majalisu. Abin nufi Sarki ya fuskanci Siyasa a Majalisarsa irin ta Majalisar Wakilai inda da tarin quri'u ake zartar da komai.

Ko Sarki ya nemi shawarar 'yan Majalisarsa ba zai iya zartar da komai ba sai da izinin Razdan wanda shi ne ke riqe da kambun muxlaqin Sarakuna. Don kuwa idan Sarki zai riqa tuntuvar 'yan Majalisar ba Razdan ba, yin hakan zai kawo wa *Indirect Rule* babbar illa. Duk da cewa Turawan Mulki sun jefa Sarakuna a tsaka-mai-wuya sai suka karkata hankulansu wajen goyon bayan 'yan Siyasa a gwagwarmayarsu ta rusa muxlaqin mulki. A dalilin haka ne Gwamna ya yi musu wannan kira.

Ku Nemi Shawarwarin Mashawartanku

---

[1] GTK Ta 495, 5/3/1952

A qoqarin jaddada kiran Sir Abubakar ga Sarakunan Arewa na su lizimci neman shawarwarin 'yan Majalisun ne ya sa Leftana Gwamna Sir Byan, a jawabin sa da ya yi a wajen tabbatar da Sarkin Kano Sunusi sarautarsa ya ce, "Wayo da gwanintar mutum guda xaya tak, koMai girmansa, ba za ta wadatar ba. Saboda haka, lallai ne a wajen tafiyar da ayyuka, a kowane lokaci ka nemi shawarwari mashawartanka, sa'an nan kuma kai da majalisarka sai ku yi aiki tare, cikin niyya, domin amfanin jama'a."[1] Ai akan wannan mulkin Sarakuna ya ginu, domin koyarwar addininsu ne suke neman shawara bisa kan kowane bisa kan kowane al'amari.

Haka kuma a lokacin da Leftana Gwamna ya tabbatar da Sarkin Gwandu Haruna da Sarkin Argungu Muhammadu, duk ya yi musu jawabi makamanciyar wannan. Ganin yadda Leftana Gwamna yake ta maimaita wannan Magana wadda ta qara wa ta qarfi, sai aga lallai wannan Magana za ta ja hankulan mutane gare ta, za kuma ta ja hankalin Sarki gareta.

Domin kuwa wannan abu sananne ne, komai abin mutum, in dai Musulmi ne, ajizi ne. yadda duk ya kai da sarauta, ko dukiya, ko karatu, haqiqa ba zai iya isar wa kansa ba. In yana son aikinsa da sha'aninsa su tafi dai-dai, to, lallai ne ya riqa yi yana shawara da waxanda suka kamata ya yi shawarwari da su. saboda haka, maganar Sir Bryan Sharwood Smith ba baquwa ba ce a Arewa, domin neman shawarwari daga mashawarta wajibi ne a tsarin mulkin Sarakuna na asali. Amma Turawa sun yi wa wannan tsari karan-tsaye a qoqarinsu na rusa tsarin masu ba Sarki shawara da zavavvun Mashawarta waxanda za a iya sauya ra'ayinsu ta hanyar yin amfani da kuxi ko muqami.

Idan aka dubi tarihin sha'anin mulkin Fulani a Jihar Arewa, za a tarar shugabannin farko ba su qulla komai, sai da shawartar mashawartansu. Ba su rushe komai, sai bayan shawarwarinsu ta gamu a kan rushewar it ace alheri.[2]

Amma waxannan Mashawarta sun yi ficewajen tsoron Allah da nuna dattako saboda muqamansu na gado ne kowannen su kuma yana kishin gidansa da masarautarsa.

Dimokuraxiyya ta hudo kai a Arewa da zuwan Turawa, saboda haka babban burin kowa, shi ne a ga cewa abubuwa suna tafe cikin tsari mai kyau. A ga jama'a sun sami bakin Magana a cikin kowane abin da ya shafe su. Har ma ana da burin a

---

1 GTK Ta 495, 23 Yuni, 1954.

2 *Ibid*. 23 Yuni, 1954.

sakar musu waxansu abubuwa waxanda za su iya yi da kansu, ba lallai komai sai a yi musu ba sai ka ce jarirai. Ko da yake tsarin Sarki-Cikin-Majalisa ya karya gadon bayan sarauta ne domin ta zaizaye qarfin ikonsa. Amma qarfin shugaba a Majalisar Wakilai kuwa yana nan dimirmir. Saboda haka ta ba shi ikon 'Sayen' 'yan Majalisar da kuxi ko muqami don ya samu gabatar da shiri da manufofinsa ba tare da matsala ba.

Dalili ke nan gwamnatin Jihar Arewa ta shirya kakkafa majalisu iri-iri, ta yadda in an tako mataki, Magana za ta isa ga Hakimi, ta isa ga Sarki. Sarki kuma ga tasa majalisar. Amma idan masu adawa da Sarki suka so suna iya 'Sayen' 'yan Majalisar Sarki wato mashawartansa don su dagula al'amuransa domin ba shi da cikakken iko, a Majalisarsa.

To, ga tsammanin jama'a, abin da wannan kalami nasa, shi ne ya san Karin maganar Hausawa da su kan ce, "Ruwa halin qasa yake bi." Watau idan Sarki ya zama ba mai yin shawara da majalisarsa za su zama, haka dangatakarsu za ta zama. Haka kuwa sauran jama'arsa za su zama. Idan qasa ta zama kowa yana ji da kansa ne, domin mulkinsa, ko dukiyarsa, ko iliminsa, to qasar nan sai dai ta yi ta komawa baya. Allah Ya nuna mana ci gaban Arewa a bisa tafarkin alheri, amin.[1]

To, amma ba a nan ne Gizo ke saqarsa ba. Leftana Gwamna Sir Bryan, yana nanata wannan jawabi ne domin maganar shawara da mashawarta ta karvu a zukatan jama'ar Arewa. Idan haka ya samu sai a turo wasu "Mashawarta" 'yan Siyasa waxanda za su zo su damamushe mulkin Sarakuna gaba xaya. Saboda 'yan Arewa ba su san Dimukuraxiyya ba ballantana su san illolinta.

Sarakuna sun tsinkayi zuwan wannan al'amari. Don kuwa sun lura da take-taken Mai Wandon Qarfe, musamman ganin yadda ya rubuta wa Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayero CMG, CBE., wasiqa ta musamman, a kan sabon mulkin da yake son gani a mulkin Sarakuna. Ya rubuta wannan wasiqa a Febrairun 1953 saboda wataqila yawan qorafin da 'yan Siyasa ke yi na mulkin mutum guda. Sun daxe suna wannan qorafi cewar masu yawan miliyon uku? Duk da cewa a wannan lokacin mulkin Sarauniyar Ingila ya wuce na qasar Ingila, na kusan duniya ne baki xaya. A cikin wasiqar da Leftana Gwamna Sir Bryan Sharwood Smith ya aika wa Sarkin Kano bai voye goyo bayansa ba ga masu fafitikar rusa muxlaqin mulkin Sarakuna. A cikin wannan wasiqa ne ya ce: "abin baqin ciki ne da lokaci ya wuce na mulkin mutum guda shi kaxai qwal ba tare da taimakon hikima da

[1] GTK Ta 23 Yuni, 23 Yuni, 1954.

gogewa da ikon wasu mutane a harkokin mulkin Kano ba. Saboda haka tilas ne in shaida maka da ka xauki shawarar da ni da Razdan ke yawan baka na a qara sanya sabbin jini cikin 'yan Majalisarka saboda a qara mata karsashi, ta zama mai iko da kanta da kuma karvuwa ga duk mutanen Kano muhimmai kuma amintattu a idon jama'ar Kano."[1]

Sir Bryan Gwamna wanda ya laqanci hulxa da jama'ar Arewa babu kuma Gwamna wanda ya naxa ya kuma sauke Sarakuna kamarsa. Shi mutum ne Sakaina mai iya ruwa. A bisa tsarin mulkin mallaka ya zama tilas ya juya wa Sarakuna baya waxanda yawancinsu sun xauke shi a matsayin uba kuma wani bango mai qarfi wajen jingina. Wannan wasiqar ba za ta bai wa Sarkin Kano mamaki ba saboda guguwar yaqi tsakanin Sarakuna da 'Yan Siyasa ta daxe da turnuqewa. Amma duk da haka ana iya cewa Mai Wandon Qarfe ya ci amanar Sarakunan Arewa, waxanda ba su da na biyu wajen nuna biyayya da bada taimako ga Sarauniya. Wasiqar da Sir Bryan ya rubuta wa Sarkin ya yi ne a kan jita-jitar da yake ji don kuwa Kanawa na bin Sarkinsu ne sau da qafa, saboda mulkin Sarkin Kano Abdullahi Bayero na ciyar da qasarsu gaba ta fuskoki daban-daban. Shi ma gwamnan ya shaida wannan batu domin ya ce:

In mutun ya dubi rkice-rikicen da ke tafasa a Kano a lokacin sai ya gane cewa, abin da ya sa zaman lafiya a garin shi ne samun Sarki irin Abdullahi Bayero. Ga shi da ya tsufa, amma hikimar mulki da wayon tafiyar da shi sai wanda ya zauna tare da shi zai iya fahimtarsa. Ga shi da ilimi mai zurfi na Muhammadiyya. Ba abin da yake vata masa rai kamar yadda yake ganin halin yaran zamani na ta lalacewa. Yara ba sa girmama manyansu. Ba a bin da suka sa a gaba sai su sami kuxi su sheqe ayarsu. Kowane mako, sai ya fito qofar Kudu, ya zauna filin Allah. Mace ko namiji mai kuka, ko qara, ya taho wurinsa kai tsaye. Bawan Allah! Ga shi a fili yana qoqarin taimakon jama'a, amma a yadda muka sami rahoto, an cewai yana tashi, sai fadawa su jujjuye duk maganar da aka yi, don a ba su rashawa.[2]

Duk Sarkin da ya kawo wa qasarsa zaman lafiya kamar yadda Sarki Abdullahi ya yi, ai ko shakka babu yana da amintattun 'yan Majalisa. Hausawa sun ce 'gani ya kori ji'. Sir Bryan ya san Kano tun daga shekarar 1924 na tsawon lokaci.

---

1 CO 554/236/37/02, *Reform of Local Government in the Northern Nigeria* (1952-54).

2 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 54.

Saboda bai kamata ya xauki rahoto na "an cewai yana tashi sai fadawa su jujjuye duk maganar da aka yi." Kowane Sarki yana tare da wasu fadawa marasa kyau. Ba Sarkin da zai ce ba shi da su. Har ila yau wannan Leftana Gwamna ya yi iqirari da cewa:

Na sami Kano cikin babban rikici. Birnin kamar a ce yana rabe ne kashi biyu. Ga hayin Fulani, wato inda masu mulki suke, ga kuma hayin Have inda Kanawa na asali suke. To, tsakanin su sai na samu babu shiri sosai. Sai dai qarfi ne ke danne da tanqwasa. Saboda haka na shiga qoqarin bai wa Sarkin Kano shawara ta ya yarda ya sanya Haven nan a cikin Majalisarsa.[1]

Sir Bryan ta haka ne ya riqa shisshigi da katsaladan a cikin harkokin mulkin Sarakuna. Wataqila domin yana taqama da cewa shi ne ya naxa Sarakuna masu yawan gaske, don haka yake qoqarin sauya tsarin mulkinsu. Amma ba don ya inganta su ba sai don ya shigar da muguwar siyasa a cikin wadda za tarwatsa su. Saboda tsarin mulkin mallaka ne ya kau da al'adu da xabi'un al'umma ya kuma cunkusa masu na Turawa. Idan kuma an samu dama a raba su da addininsu ko kuma a birkita masu shi. Akwai qasashe masu gidajen Sarauta daban-daban kamar Kano, amma babu inda aka sami wani babban rikici wanda zai kawo cikas a ci gaban wannann Masaurauta. Wannan Bature ya yi qoqarin rusa majalisar Sarkin Kano saboda ita ce ta tsole masu ido sosai: "Mutane miliyan uku na bin mutum guda sau da qafa!" Amma shirinsa ya ci tura saboda Sarkin Kano Abdullahi ya yarda ya sanya Alhaji alhasana Xantata, Mashahurin xan Kasuwa ya shiga Majalisarsa, ba don komai ba sai don shi Alhaji Alhasan Xantata dattijo ne mai gaskiya da riqon amana.[2] Wataqila wannan Mashahurin Sarkin ya gane Mai Wandon Qarfe yana qoqarin ya haddasa rikici ne a tsakanin Fulani da Have a cikin Majalisarsa. Don haka ya yi biris da kata-katar da wannan Bature ke yi da wasiqar da ya rubuto masa ba don komai ba sai don ya rusa masa Majalisa.

Har'ila yau a shekarar 1953 ne batun naxa Ministan Qaramar Hukuma ya taso wanda Sarakuna suka harari shirin saboda Sarakuna sun yi dabur a wannan lokaci. Amma da aka kwao batun a Majalisa sai Sarkin Musulmi ya amince da shi ba tare da wata jayayya ba. A dalilin haka ne Sarakuna su ma suka amince da shi baki xaya.

---

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 54

[2] *Ibid.*

Duk da haka sai da Sarkin Gwandu Yahaya (wanda daga bisani ya zama Sir ya bayyana dalilin tsoronsa ga naxa Ministan Qaramar Hukuma. Wannan Sarki tsohon xalibin Kwalejin Qatsina ne wanda ya fi duk manyan Sarakuna ilimin Zamani. Shi da Sarkin Zazzau sun goyi bayan Sarkin Musulmi. Amma Sarkin Gwandu sai da ya yi wa tufka hanci ya ce duk wani muqami da ikon da wannan Minista zai samu sai fa an tuntuvi Sarakuna. Sarkin ya ce, "mun ji tsoron wannan batu da aka gabatar mana." Sarki Yahaya ya qara da cewa:

> Ba mu ce ba mu son Ministan Qaramar Hukuma wanda zai dinga rangadi don duba ci gaban qananan cibiyoyin mulki. Abin da muke qi shi ne a xora Ministan a kan Sarakuna ... ko kaxan ba ma son a bar Arewa a baya, muna kuma qin ragewa Sarakuna daraja da iko, ko kuma a xora wannan Ministan bisa kansu. Wannan ita ce manufarmu.[1]

Sarkin Gwandu Sir Yahaya, qasaitaccen Basarake ne qifaxi wanda a zamaninsa ya sami yabo daga jama'arsa da mutanen Arewa baki xaya. A lokacin rayuwarsa ne ya sami laqabin "Mai Gaskiya" saboda yana da zurfin ilimi da dattaku da tawali'u. Amma abin da ya hango shi ke tafe, wato ragewa Sarakuna daraja da iko da kuma mayar da su qarqashin Ministoci.

Duk da qoqarin da Sarakuna suka yi na ganin wanda ya riqe Ministan Qaramar Hukuma Basarake ne amma saboda zagon qasa da Mai Wandon Qarfe ya riqa yi masu sai da suka koma qarqashin Ministoci. A matsayin Mashawarta.saboda haka da *Indirect Rule* ya zo qarshe sai mai doki ya koma zayi. Tun daga wannan lokaci ne kadarin Arewa ya karye zamani kuma ya shiga watangaririya da jama'a. Ruwan da ya ci Sarakuna shi ne ya ci Makarantun Alqur'ani.

Tarkuna uku da aka xana wa Arewa sun yi mata mugun kamu sune kuma suke lalata harkokinta har yanzu. Idan aka yi nazarin matsalolin da suka dabaibaye Arewa, a lokacin kafa sabuwar Nijeriya, za a ga illolin Mulkin Mallaka ne suke fito wa fili a wannan zamani, 'yan Siyasan Farko sun kixime saboda ganin masifu kewaye da su ta ko'ina. Amma duk da haka sai da Sardauna ya yi ayyuka muhimmai waxanda suka fito da Arewa zuwa wani fagen da ta isa a yi da ita a Nijeriya. Saboda hikimarsa da fahimtarsa ta siyasa da Sarakuna ya yi namijin qoqari wajen samar da haxin kan Arewa. A lokacin sa, Arewa sai ta zama tsintsiya maxaurinki xaya. Amma siyasa da Sarakuna ta xauki sabon salo bayan samun mulkin kan Nijeriya wato a qarshen Mulkin Mallaka.

---

[1] HCD, 14 ga Febrairun 1953, shafi na 78-79.

Qarshen *Indirect Rule*

A ran 1 ga watan Oktoba na shekarar 1960, Nijeriya ta samu 'yancin Kai. Wannan 'yancin Kai ya taho da taqaddama musamman a fannin tsari. A Nijeriya ta Arewa, Iko a kan tsarin En'e ya baiwa Sarakuna damar tantancewanda yake da Iko da gwamnatin yanki. Don haka sai suka yi dabara suka kankane ikon da suke da shi a matakin Qaramar Hukuma na qoli da kuma neman zave zuwa ofisoshi na yanki da na qasa na 'yantakara, waxanda tun haihuwarsu ko matsayinsu na siyasa suka sanya suna mutuntawa da kuma Martaba gidajen sarauta. Su kuma a nasu vangaren suna sa ran gwamnati ta saka masu ta hanyar kaucewa sanya baki a sha'anin gudanar En'e-En'e. Sarakuna da dama suna yi wa 'yancin Kai kallon wata dama ta qara iko da kankane harkoki fiye da a lokacin da ake qarqashin Mulkin Turawan Birtaniya su kuma 'yan Siyasan sun qosa su nuna cewa gwamnatin yanki ta fi qarfin dukkan En'e-En'e, wanda wani tsari ne da ya qunshi gagarumar sanya ido, da sanya baki ko katsalandan, ga gudanar da mulki na Qaramar Hukuma. Jim kaxan da samun 'yancin Kai (1960-1965), shekaru ne da ke cike da yawan sa bakin gwamnati cikin sha'anin gudanar da sarautu da Qaramar Hukuma, a wasu lokutan ma ta kai ga tsige Sarki ko yi masa takunkumi.[1] Ko da Nijeriya ta samu 'yancin kai babu wani mataki muhimmi da aka xauka na ganin an yi maganin illolin Tarko Uku da suka ci Arewa. Saboda har yanzu tsarin Mulkin Mallaka ake bi, sai dai inda ya zama tilas ayi gyaran fuska. A wannan lokaci ne 'yan Siyasa suka lura da cewa ya zama wajibi su huda kwamin Majalisar Sarakuna domin na su kwamin ya kai ga gaci. Don in ba haka suka yi ba Sarakuna na iya dawo da qarfinsu na *Native Sole Authority* wanda yin haka zai maida 'yan Siyasa su tashi a tutar babu. Su koma baya a qoqarinsu na maye gurbin muqaman Turawan Mulki.

A shirye-shiryen samun 'yancin Kai, Firimiya, Sir Ahmadu Bello ya nunawa En'e-En'e cewa gwamnatin cin gashin Kai za ta qasance, za ta zama gaba xayanta qarqashin kulawar gwamnatin Yanki, wato Jihar Arewa da ke buqatar babbar darajanta qwazo da gaskiya. A watan Agusta na shekarar 1958, a lokacin da ake tafka muhawara a Majalisar Sarakuna akan qudirin samun 'Yanacin Kai, Sardauna ya shata layin taqaddama, ya kuma yi gargaxi da cewa:

> *Ina so in isar da wani muhimmin saqo ga hukumomin En'e, gwamnatin cin gashin kai na nufin hukumomin En'e za su xauki qarin nauyi, kuma mai yawan gaske; babu mamaki wasunsu su xauka cewa za su samu damar ci gaban kansu, su yi watsi da gwamnatin yanki; in haka suke xauka, ina so in kawar masu da wannan mafarki yanzu kuma a nan. gwamnatin yanki ke da iko kuma za ta ci gaba da zama*

[1] A.M. Yakubu, *An Aristocracy in Political Crisis*, shafi na 180

mai iko. Da gaske nake yi da na ce gwamnatin yanki ta qudiri aniyar gudanar da Mulkin Yanki. Kada ma mutum ya fara tunanin akasin hakan.[1]

A qarqashin Mulkin Ingilishi gwamnati na iya kau da idanunta daga harkar mulkin Qaramar Hukuma muddin dai Sarakuna na ci gaba da yin biyayya babu wani kace-nace. Da aka samu yancin Mulkin Kai, Sarakuna da dama sun yi qoqarin ci gaba da hakan ta hanyar tunanin cewa goyon bayan siyasa da suke baiwa gwamnatin NPC tamkar wani tabbaci ne na xorewarsu da kuma 'yancin xaukar mataki, koda kuwa kyakkyawan mulki aka yi a Qaramar Hukuma. Sai dai a wannan karon, goyon bayan siyasa, tare da watsi da aikata gaskiya ba abu ne mai yiwuwa ba. gwamnatin yanki ta fi xora muhimmacin akan aikata gaskiya. Ko da yake Sarakuna sun so mulkinsu ya daxe ta mara wa Jam'iyyar N.P.C. baya kamar zamanin *Indirect Rule* amma yaqi da Sarakuna da 'yan Siyasa suke yi bai ba su damar cimma wannan manufar ba. Domin kuwa 'Yan Siyasa sun ci gaba da aibanta Sarakuna da laifin rashin aikata gaskiya saboda sun fahimci cewa da wuya su maida Sarakuna qarqashin ikonsu

A wannan lokaci ne, gwamnatin yanki ta nuna a baki da kuma a aikace cewa, gaskiya ce kan gaba da duk wata biyayya ta siyasa, Ko da yake ana sane cewa ba ka iya raba su biyun da juna. NPC na goyon bayan tsarin En'e, su kuma jama'a masu kaxa quria a matakin Qaramar Hukuma na ci gaba da qara amfani da qwazo da En'e ke yi a matsayin ma'auni na auna qwazon gwamnatin Yanki. A cikin ita kanta gwamnatin ana nuna tsoro a fili cewa rashin qwarewar En'e ko shakka babu a qarshe ba zai haifarwa siyasar NPC kyakkyawan sakamako ba. Misali, an gano cewa a lokacin zavavvuka na Tarayya na shekarar 1959, masu zave sun fi mayar da hankali ne a kan batutuwa na cikin gida da suka fi shafar al'umma.Tunda En'e-En'e a siyasance na tare da gwamnati, akwai rashin gamsuwa a quri'u da dama, (Ko da yake ba ta wakilai da aka zava ba, domin kuwa yawanci 'yan takaran NPC ne ta jam'iyyun siyasa 'yan adawa. Zavar 'yan takara 'yan adawa ana xaukarsa tamkar dawowa daga rakiyar En'e-En'e ne a kaikaice, da ma ita kanta gwamnatin.[2]

Samun `yancin Kai ya baiwa 'yan siyasa damar da suke nema. A wannan lokaci mulki zai koma hannunsu kacokan. Saboda haka za su yi amfani da qarfin ikonsu su durqusar da mulkin Sarakuna, wani muxlaqin mulki da ya daxe yana ci masu tuwo aqwarya. Saboda haka zuwan wannan lokaci, ai nasara ce babba a yaqin Qwatar `yanci.

---

1 A.M. Yakubu, *An Aristocracy in Political Crisis*, shafi na 180-181

2 NAK/MLG.4117: B. Greatbatch. Secretary to the Premier, to all Resident. No PM. 243/4, Para. 2A Ile.

Qarshen Mulki ta kan Sarakuna ya zo, zai kuma tafi ya bar Sarakuna da rashin madafa. Ko da yake sun yi qoqarin su dafa jam'iyyar NPC, amma alqalami ya bushe, yaqin Qwatar yanci ya kai ga nasara. gwamnatin yanki zata saurarawa Sarakuna amma kuma ba zata rangwanta masu ba. Ayya! Ashe rusa muxlaqin mulkin Sarakuna domin kafa muxlaqin mulkin 'yan. Siyasa durkusar da Arewa zai yi!

Domin amfanin gwamnatin yanki, dole a xauki mataki akan En'e-En'e da ke kauce hanya ba tare da la'akari da goyonbayana siyasa da suka bayar ada kuma suka ci gaba da bayarwa ba. Abin da ke gaban gwamnati shi ne yadda za ta hana ma'aikatan En'e shiga harkar siyasa, tunda an amince da hakan a qa'idojin aikin ma'aikata. gwamnati bata vata lokaci ba wajen haramta wa Sarakuna shiga harkar siyasa. Domin `yan siyasa su samu damar cin karensu babu babbaka. Amma kuma yin haka ya kaucewa tsarin siyasa. An yi haka ne don a tabbatar da cewa Sarakuna basu sami fiffiken qara tashi ba.saboda haka aka yi masu tarnaqi a cikin Majalisarsu sa'an nan aka haramta masu canza sheqa zuwa Majalisar Siyasa. Da nufin ikonsu da martabarsu za su zaizaye a hankali.

Ko da yake Sardauna mai ra'ayin Siyasa da Sarakuna ne, amma lokaci ya yi da goyon bayansa ba zai xore ba saboda 'yan adawa da Sarakuna sun yi qarfi sosai, suna kuma ganin wannan lokacin su ne da za su zaizaye qarfin muxlaqin mulki. Idan 'yan siyasa ba su yi amfani da damar da suka samu ba, to, ba za su sami wata makama ba tunda mulkin En'e ya kan kama a ko'ina. Hasali ma dai, a wannan lokaci Sarakuna basu da goyon bayan Turawan Mulki. Qarshen *Indirect Rule* sai ya ba 'yan siyasa wata babbar damar rusa muxlaqin mulki, abin da suka kuxiri niyyar aiwatarwa tun suna makaranta. Saboda haka wannan gwagwarmayar qwatar 'yanci ba ta shafi talakawa ba. Yaqi ne da 'yan siyasa suka xauka akan Sarakunansu. A dalilin haka ne ma aka kafa dokar da ta haramta wa ma'aikata shiga harkar siyasa. Ita wannan doka ta baiwa 'yan siyasa galabar da suke nema ruwa a jallo. Ita wannan doka da ke cewa:

"Ba a yarda ma'aikaci in ba ya nemi izini daga hukumar En'e ba, ya shiga duk wata harka ta rikita rikitar siyasa, da kuma faxin dukkan wani ra'ayi da ya savawa tsarin En'e. In ya yi haka laifi ne da ya savawa xa'a."[1] Farfesa A.M Yakubu ya yi bayani akan wannan doka, inda ya ce:

"A fili bayanin na nuna cewa ma'aikacin En'e na iya shiga siyasa da izinin manyansa. Tunda a lokuta da dama, dukkan hanyan jami'an En'e an taka muhimmiyar rawa da su a siyasa, kuma tunda su ne gwamnatin En'e, duk abin da suke yi sai da izini kuma ya yi dai-dai da qa'idar aiki ta ma'aikatan. Tunda

[1] A.M. Yakubu, *An Aristocracy*, shafi na 182.

dukkan ma'aikatan Qaramar Hukuma sun shiga siyasar NPC ka'in da na'in ya sanya wancan vangare na qa'idar aiki ta ma'aikaci, da ke hana shiga badaqqalar siyasa da faxin albarkacin baki da ke sukar tsarin En'e, ya zama ba shi da tasiri. Bugu da qari mene ne laifin da ya savawa xa'a abu ne da ba a fayyace shi ba. Muhimmi dai gwamnatin 'yanki ta na son cin ribar shigar ma'aikatan En'e siyasa. Saboda haka matsalar a nan ita ce yadda za a yi haquri da hakan ba tare da an yi watsi da kyakkyawan tsarin Qaramar Hukuma mai gaskiya da adalci. Batu ne na mulkin En'e da dangantakarsu da gwamnati, ba batun shigar ma'aikatansu siyasa ba wannan shi ne abin da gwamnatin yanki ta fi mayar da hankalinta a kai.[1]

Abin da wannan dokar ta haifar daga shi ne xan siyasa zai iya samun muqamin muqamin sarauta amma Basarake komai dacewarsa an haramta masa duk wani muqami ko matsayi dake da alaqa da Siyasa. Sai aka dankwafe Sarakuna a gefe guda, a matsayin "Iyaye al'umma" waxanda Siyasa ta haramta a gare su! Wannan tsari ne da ya kaucewa Siyasa kanta. Domin kuwa an taqaita wa jama'a wajen da za su zavi mutanen da suke son su wakilce su. Amma an kafa wannan dokar ne wataqila, don tsoron kada Sarakuna su yi qarfi a Siyasa su dawo da martaba da ingancin Sarauta a Arewa, irin Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato. Kafin akai ga 'Yancin Kai, wanda ya kawo qarshen mulki takan Sarakuna, siyasa da Sarakuna duk da tangarxarta ta yi kyakkyawan tasiri a ci gaban Arewa. Saboda Sarakuna na sa ido da tsawatarwa akan ayyukan 'yan Siyasa. Haka suma 'yan siyasa kan takawa Sarakuna birki a lokacin da yin haka ya dace. A wannan lokaci akwai matsakaiciyar adawa a tsakanin Majalisar Sarakuna da ta Wakilai saboda Turawan Mulki sun sa ido suna kuma dai-daita al'murran Arewa, kamar alqalan wasa. Amma da Nijeriya ta samu 'yanci sai maitar 'yan siyasa ta fito fili sosai. Suka kumma tashi haiqan wajen ganin cewa sun tuge Tutocin Shehu Mujaddadi. A kuma yaqin da suke yi da Sarakuna na qwatar 'yanci ba sa la'akari da ci gaban Arewa. Abin da suke hanqoran samu su qwata shi ne su qwato muxlaqin mulki ya koma hannunsu, ba domin komai ba sai don su ci karensu babu babbaka. To, da muxlaqin mulki ya koma ga 'yan siyasa sai mulkin Farar Hula ya shiga tavarvArewa tun daga wancan lokaci har yanzu. Amma kafin su kai ga cimma wannan nasara, sai da suka yi qoqarin su sauyawa Sardauna ra'ayi akan Siyasa da Sarakuna da yake qoqarin murjewa don ta tafi da zamani.

A watan Yuli na shekarar 1960, Firimiya ya rubuta wasiqu guda biyu, xaya ga Kansiloli guda dubu xaya da saba'in da xaya (1,071) da ba zavavvu ba (na gargajiya da waxanda aka naxa), xayar ga kowanne Kansilan da aka zava su dubu xaya da ashirin da tara (1,029). Saqon da ke cikin kowanne ya yi kama da juna.

[1] A.M. Yakubu, *An Aristocracy*, shafi na 182.

An tunatar da Kansilolin muhimmancin aikinsu ga ci gaban yankin, ya kuma yi kira gare su, da su kula da babban nauyin da ya rataya a wuyansu. Jigon saqon na Firimiya shi ne buqatar aiki tsakani da Allah, vangaren kuxi da na mulki. Amma ya jaddada cewa za a yi aiki da ikon gwamnati inda aka ga an yi lallashi amma abin ya gagara ya ce: "Idan ba ku xauki shawarata ba, zan yi amfani da ikon da doka ta ba ni amma ba don son raina ba."

Ayyukan da hukumar za ta gudanar sun haxa da: Dubawa ko Yin nazari tare da ba da shawarwari yadda za a inganta qwazon vangarorin En'e a masarautar Zazzau ta la'akari da: Majalisar En'e da tsarin Mulkin tsakiya; Ma'aikata, ciki har da waxanda ke zaman kashe wando, su kuma ma'aikatan da ake da su a duba yadda aka xauke su aiki da qarin girma; Sanya ido da kuma tafiyar da kashe kuxaxen En'e;

Sardauna bai cire ran za a sami kyakkyawan dangantaka tsakanin Sarakuna da 'yan siyasa, har a bayan samun 'yancin Kai ba. Amma qarshen mulki takan Sarakuna ya qara wa 'yan Siyasa qarfi da karsashi saboda haka ne sai, mulkin Sarakuna ya shiga tavarvArewa, wani hali da ya sa Sardauna yin wannan jawabi a shekarar 1962. A wannan lokaci an tashi haiqan wajen yin kamfen vatanci akan Sarakuna da mulkin En'e. Saboda yawan qorafe-qorafen da ya riqa samu daga 'yan siyasa, domin a wannan lokaci an yi amfani da muqami da kuxi wajen vata mulkin En'e da zargin cin rashawa da tafka almubazziranci da kuxin jama'a.

Bayanin da Firimiya Sir, Ahmadu Bello ya yi ga Majalisar Sarakuna a game da dangantaka tsakanin gwamnati da Hukumomin En'e a shekarar 1962, inda ya ce:

> *Mai girma shugaban qasa, na tabbata 'yan wannan Majalisa kun ji kalaman da na yi a Majalisar Dokoki a game da dangantaka tsakanin gwamnatin yanki da hukumomin En'e. Ina sane cewa wakilan wannan Majalisar suna nan sun qosa su ji me ya sa aka yi waxancan kalamai, da yadda kalaman suka shafe su. Ina jin gwamnati za ta so ta ji wakili xaya ko biyu su faxi wani abu idan suna da wata gudunmawa da za su bayar.*
>
> *An sanar da gwamnati damuwar da, da dama daga cikin 'yan Majalisar Dokoki ke da ita, a game da danganta tsakanin gwamnati da wasu hukumomin En'e. An bayyana tsoron cewa wasu hukumomin ne En'e sun yi qarfi har sun fara yin kunnen uwar shegu da umarnin gwamnati. Ba a Majalisar Dokoki kawai ke nuna wannan tsoro ba, har a wajenta a cikin sauran jama'a musamman daga wasiqun da ni qashin kaina nake samu a kullum da ke roqon a kafa wata hukumar binciken wasu hukumomin na En'e.*

Bayan waxannan wasiqu na zahiri basa xauke da sanya hannun waxanda suka aiko da su, ina kuma samun wasiqu a kullum sun fi a qirga da babu suna babu sanya hannu, da ke zargin hukumomin En'e, da Ma'aikatu, da Ministoci da ni kaina na aikata ba dai-dai ba nan da can.

Ina son in yi amfani da wannan dama in yi nuni ga jama'a ta hannun wakilai cewa irin waxannan wasiqu da ba a san su wa ke rubuta su ba, ba su da wani amfani. Ya kamata duk kanmu mu zama marasa tsoro, da zama a shirye don yi wa qasarmu aiki tsakani da Allah. Lokaci ya yi da ya kamata mu amincewa juna da amana. Duk wanda yake son ya rubuto mun, ya rubuta xauke da sunansa na gaskiya da adireshi domin in iya gudanar da cikakken binciken zargin da aka yi.

Saboda wannan tsoro da ake nuna wa a Majalisar Dokoki da ma a sauran jama'a, ni da abokan aikina (takwarorina na aiki), muna ganin ya zama wajibi mu yi qarin hasken yanayi da tsarin wannan gwamnati ga hukumomin na En'e.

Idan En'e ta baiwa wannan gwamnatin haxin kai, tana kuma gudanar da umarni babu vata lokaci, da aiwatar da Mulki, da ko daxaxa wa mutanen yankin, ita kuma wannan gwamnatin a nata vangaren za ta baiwa hukumomin En'e dukkan wani taimako da agaji (tafi).

Idan kuwa wata hukuma ta En'e, waya Allah babba ce ko qarama, ta gaza aiwatar da umarnin gwamnati ko gudanar da mulkin yankinta kamar yadda ake buqata, to fa gwamnati ba za ta yi wata-wata ba wajen xaukar qwaqqwaran matakin qarfi da yaji domin shawo kan wannan matsala. Misalan, inda aka xauki irin waxannan matakai su ne Argungu, da Zariya, da Zuru da Ningi waxanda 'yan kaxan ne na ambato. Ba sai na tsaya ina sake faxin matakin da gwamnati ta xauka a kowanne ba. Bari in sake fayyace maku cewa wannan gwamnati ta qudiri aniyar gudanar da mulki, da burin ganin an aiwatar da umarni da tsare-tsarenta. gwamnati ke da qarfi da iko kuma za ta neme su a duk inda suke. (tafi).

Matakin da gwamnati za ta xauka, in har ya zama dole a kan hukumomin En'e da suka yi qoqarin watsar da wannan umarni (yin kunnen uwar shegu), zai danganta ga irin yanayin da ke wajen. A inda abin ya yi tsanani, gwamnati na iya in har ya zama dole, ta rushe wannan hukumar ta En'e. Za a iya haxe qananan hukumomin zuwa manya idan buqatar hakan ta taso. Haka zalika manyan

hukumomin En'e za a iya karkasata zauwa qanana idan ya zama wajibi a yi hakan.

Saboda haka kowa ya fahinta wannan gwamnati ba ta tsoron wata qaramar qungiya tana dai haquri ne. Za ta sauke nauyin da ke wuyanta da kuma sanya qafar wando guda da dukkan wani sashe ko mutum da ka iya qoqarin sanya qafa ya shure tsare-tsare da umarnin gwamnati. Waxannan tsare-tsare da umarni dukkansu ana yi ne saboda burinmu da kuma haqqin da ya rataya a wuyanmu na kawo gudanar abubuwa gadan-gadan, da adalci da kuma kyautata rayuwar dukkan jama'armu, da kawar da dukkan wani nau'i na nuna bambanci da rashin iya mulki, da rashawa, da fatara a koma ina ne suka yi saura. Mun qudiri aniyar sauke wannan nauyi da tarihi da yanayi na yau da gobe ya xora mana. Dukkan wanda ya yi qoqarin hana mu, ya yi wa kansa faxa.

A nan Mai girma Shugaban Qasa, ina so in tunatar da masu girma a nan Majalisa cewa, shekara xari da hamsin da suka wucewasu mutane ne ke mulkin Qasar nan da a yanzu suka zama wani vangare na tsarin En'e. Sun sanya qafar wando guda ba ko tausayawa ga waxanda suka yi wasa da mulkinsu. Birtaniya ta gaje su (na) wasu shekaru hamsin da tara, inda suka yi mulkin Qasar nan a ta hanyar da suke ganin ya dace da tsarinsu na adalci. A yanzu tarihi ya maimaita kansa da 'yan qasa suka gaji Birtaniya, saboda haka ba sa buqatar komai daga 'yan uwansu illa haxin kai.

Ina fatar wannan bayani ya isawar da dukkan wani duhu ko tababa da tsoro vangaren 'yan Majalisar Dokoki, su kuma jama'a zai zame masu gargaxi ga dukkan wata hukuma ta En'e wacce ba ta fahimci ainihin matsayintaba. Sai dai bari in kammala da jaddada cewa na matuqar amincewa tsarin En'e wanda hukumomi ne na kusa da jama'a da ke tafiyar da sha'anin jama'arsu, da kuma imanin da nake da shi ga cikakkiyar biyayya ga tsare-tsaren gwamnati na mafi rinjayen hukumomin En'e. Ka da wani mutum ya yi tunanin cewa wannan gwamnati ta yi niyyar lalata wannan tsari, sam ba haka ba ne, dukkanmu muna son ci gaban dukkan wani Sarki. Ni kaina tsarin ne ya haifeni ya rene ni, saboda haka ba zan tava qoqarin sare bishiyar (itaciyar) da kakannina suka dasa ba, in har ban taimaka mata ta girma ta yaxu yaxuwar alheri ba (tafi).

Ya Allah ka yi mana jagora da karemu daga dukkan sharri. Amin.[1]

---

[1] Majalisar Jihar Arewa: Muhawara ta Sarakuna, 11 Afrilu 1962, 123-125

Jawabin Firimiya ya nuna a fili akwai wasu da suke wa mulkin Sarakuna yarfe don su baqanta shi, a yaqin su na qwatar 'yanci ido rufe, baki buxe amma kuma rusa muxlaqin mulkin Sarakuna wato tuge Tutocin Shehu Mujaddadi sai ya zama rusa Arewa suke yi saboda son rai. Arewa qasa ce mai bambanci da ban mamaki. Mulkinta yafi qarfin `yan siyasa su kaxai, sai an haxa da Sarakuna idan ana son siyasa da mulkin da ya dace da Arewa. Amma idan ba a buqatar yin haka, to, Arewa ta yi watsi da al'adunta ta koma kamar Kudu sak. Saboda mai yiwuwa yin haka ya dace da siyasa Yammacin Turai; Samfurin na Falimantare irin na Ingila ko na shugaba mai cikakken iko irin na Amurka. Ko wane tsari Nijeriya ke bi bai kamata 'yan Siyasar Arewa su ci gaba da neman Tuge Tutocin Shehu Mujaddadi ba. Ko kuma maida su kara zube don tabbatar da muxlaqin mulkinsu.

Sardauna Ahmadu ya haqiqance cewa mulkin Sarakuna zai iya tafiya kafaxa da kafaxa da mulkin Siyasa. Haka kuma ya dace. Saboda tsarin mulkin En'e, tsarin hukumomi ne na kusa da jama'a da ke tafiyar da sha'anin jama'arsu sun kuma yi ayyukan raya qasa muhimmai. Har ila-yau, shi kansa Firimiya ya xauki alwashin kare wannan tsarin mulki na Sarakuna. A dalilin haka ne ya ce:

"Ka da wani mutum ya yi tunanin cewa wannan gwamnati ta yi niyyar lalata wannan tsari, sam ba haka ba ne, dukkanmu muna son ci gaban dukkan wani Sarki. Ni kaina tsarin ne ya haife ni, ya rene ni saboda haka ba zan tava qoqarin sare bishiyar (itaciyar) da kakannina suka dasa ba in har ban taimaka mata ta girma ta yaxu, yaxuwar alheri ba."

Al'adun mutane su ne hanyoyin da ake bi ana amfani da hikimomi da fasahar mutane ta yadda aikace-aikacensu za su kyauta. To, wane amfani Arewa za ta samu idan ta tuge Tutocin Shehu Mujaddadi? Ba abin da yin haka zai haifar sai tavarvArewar xabi'u da al'adun jama'a. A duk lokacin da aka faxi batun Sarakuna ana nufin har da Makarantun Alqur'ani. Domin zaman Tarayyar Nijeriya bai kamata ya tilasta yin tarayya a xabi'u da al'adun jama'ar qasa ba.

Dole Arewa kwata ba Firimiya ba kawai, ta yi alfahari da Sarakuna saboda sun xauki fiye da shekaru dubu suna yin ayyukan ci gaban wannan makekiyar Jihar mai tsohon tarihi. A ko da yaushe suna da amfani ga wannan qasa. Har ila yau sune kan gaba a wajen Ayyukan Raya Qasa, a lokacin gina sabuwar Arewa.

KASHI NA GOMA SHA-HUXU

A Zamanin Turawa

Shugabannin Jamhuriyar farko sun tsinci dami a kala ne saboda sun tarar da ayyukan raya qasa da Sarakuna suka aiwatar ta Hukumomin En'e, da ayyuka masu yawa da gwamnati ta yi, wato Turawan Mulki. Waxannan manyan ayyuka da aka shimfixa a kusan kowane lungu a Arewa sun taimaka gaya wajen kawo ci gaban Nijeriya ta Arewa. Bilhasali waxannan ayyuka su ne harsashin ci gaba, da 'yan siyasar farko suka gada.

Ko a zamanin Jamhuriyar farko ma Sarakuna sun taka rawar gani wajen ganin an shimfixa kyawawan ayyukan ci gaba, an kuma gina jama'a ta hanyar basu tallafin qaro ilimi a qetare. A wannan zamani kuwa Sarakuna da yawa sun riqe muqamai daban-daban don ganin jama'arsu na samun abubuwan ci gaban qasa tare da more rayuwa. Amma kafin a kai ga mulkin Jamhuriya, Turawan mulki tare da Sarakunan Arewa sun kafa harsashin ci gaban qasa tare da ci gaban jama'ar Nijeriya ta Arewa. A qarshen yaqin duniya na biyu ne Nijeriya ta samu tallafin kuxin raya qasa daga qasar Ingila. A wannan lokaci ne Sarakuna suka tashi tsayin daka suka sa ido don ganin an aiwatar da dukkan ayyukan da wannan shiri ya kawo. Domin Sarakuna sun taimaka gaya wajen bada gudunmawa da taimakon Ingila a wannan yaqin. Ai wanda ya taimake ka xibar zuma shi ya kamata ya taya ka sha!

An samu matsaloli a farkon shekaru biyar da fara aiwatar da wannan shiri na raya qasa. An duqufa sosai wajen jawo hankalin jama'a don su fahimci wannan shiri su kuma cimma galaban amfaninsa. A farkon fara wannan aiki a watan Afrilun shekarar 1946, a kuma lokacin da aka fara aiwatar da shirin Raya Qasa da Jin Daxin Jama'ar Nijeriya ya fara aiki ne da qasida ta doka mai lamba No. 24 of 1945. Da yake wannan shiri shi ne kan gaba ga duk wani shirin ci gaba a Nijeriya, kowa na da wani haqqi wanda aka bayyana kamar haka:

Babu wani bunqasar qasa da zaman lafiya da qasa za ta samu sai an samu tsarin shiri mai kyau. Sai kuma an cika wasu mahimman sharuxxai. Dalilin haka ne, ba zai yiwu a sami nasarar tsarin bunqasa tattalin arziqi ba, sai da farko an fayyacewa mutane wannan shiri don su shiga ayi da su wajen samun cimma albarkatunsa.

Domin cimma nasarar wannan muhimmin shiri, da kuma buqatar da ke akwai ga jama'a da su shigo a yi da su, sun tilasta Sarakuna da Gwamnoni yin aiki kafaxa da kafaxa wajen kaiwa ga nasara. Wannan tsari sai ya zama kamar kundin aikace-aikace na shekara goma, wanda Gwamnonin wannan lokaci za su yi amfani da shi wajen shimfixa ayyuka muhimmai. Su kuma Sarakuna suna ba su

shawara da taimako wajen ganin an kai ga cimma nasara. Haka kuma su ne shaidu wajen ganin an kammala aiki, kamar yadda aka yi bayani. Babu shakka wannan sabon shirin raya qasa, ya fito da Arewa da Nijeriya baki xaya daga wani mummunan qangi da ta samu kanta bayan qarshen yaqi. Da wannan tabarau ne za a duba jawabin Gwamnoni da ayyukan da suka yi da kuma zunzurutun kuxin da suka kashe. Ya kamata a godewa gwamnatin Ingila da wannan gumzar da ta baiwa Nijeriya. A kuma godeya Gwamnoni da Majalisar Sarakuna da 'yan Majalisar Wakilai waxanda suka nuna kishin qasa da qin kansu wajen dagewa da sadaukar da kawunansu da suka yi wajen kafa babban harsashin ci gaba ga Nijeriya.

A dai-dai wannan lokaci da ake shirye-shiryen aiwatar da qasaitaccen shirin Raya qasa da jin daxin jama'a, sai lokaci ya yi halinsa. Lokacin da Gwamna Sir Theodore Adams (1937-1943) ya yi da zai yi ritaya.

A cikin watan Maris xin shekarar 1943, gwamnan Kaduna Sir T.S. Adams ya bar Kaduna. Ya shiga jirgi ya tafi Ikko. Daga nan zai shiga jirgin sama ya bi ta Amirka zuwa Ingila. Ya bar Nigeriya ke nan xungum, ya yi ritaya zai koma gida ya huta. Arewa sai tayi masa fatan Allah Ya kai shi lafiya, ya qara masa tsawon rai da kwanciyar hankali, ya kuma saka masa da alheri yadda ya taimaki jama'ar wannan jiha.

Sir Adams, tun cikin watan Afrilun shekarar 1937 ya zo Arewa daga qasar Malaya, ya kama aikin gwamnan Kaduna. A zamaninsa ne aka haifi Gaskiya Ta Fi Kwabo. Shi ma ne ubanta. Tun haifuwarta yake rungume da abinsa kankan. Ya buxe wa ma'aikatan wannan jarida hanya, yace duk shawarwari da jama'a suka bayar a gaya masa. Haka kuma duk tambayar da jama'a suka yi duk, im basu iya ba da amsa, to, akai masa shi zai amsa. Ya yi mulki a cikin zamani mai wuya a lokacin yaqi, amma duk da haka bai gaji da wahalhalun jama'arsa ba.

Tun zuwansa Nijeriya yake ta qoqari a qara gyara zaman ma'aikatan En'e kuma ya yi ta roqon Gwanmati da ta qara taimakon Baitulmali xinmu, don Sarakuna su iya ba da albashi mai kauri ga ma'aikatansu. To, ga shi yana gaf da zai tashi, sai Wazirin Sarkin Ingila mai lura da qasashe ya ce ya karvi wannan shawara, saboda haka ne aka daidaita albashin ma'aikatan En'e da na gwamnati.

Gurin Sir Adams ya cika.

Shi mutunme mai son yara 'Yan Makaranta, shi kuma ne ya baza dabarar tarbiyyar yaran Hausawa ta hanyar Scout, kullum kuwa yana tsaye akan taimakonsu. Ba shakka Arewa zata daxe tana tunawa da wannan Gwamna.

Da Sir Adams da Sarakuna sai ka ce abokai saboda irin wannan hali nasa ne na sakewa da mua'amala da Sarakuna har ya qara maida Sarakunan Nijeria ta Arewa duka suka zama abokan juna. Kuma shi ne Gwamna da ya sanya danqon zumunci a tsakaninsu ya qaru sosai a Nijeriya, ya fara tara waxansu Sarakuna

suna ba shi shawara in zai tafi Ikko, ya zama wakilin qasashen Arewa cikin Babbar majalisar Dokokin Nijeriya. Ya yi qoqari ainun don ya ga ba abar Jihar Arewa a baya ba, a harkokin ci gaba Nijeriya wannan ita ce addu'ar jama'ar Arewa da ake yi masa, adabo sai wata rana! Allah ba shi kwanciyar rai a wajen hutawar wannan dattijo!

To, bayan tashin Sir T.S. Adams a matsayin gwamnan Kaduna an xauki wani jigo namu, Mr. J.R. Patterson, C.M.G. (1943-1947), zai kama aikinsa. Yau shi Allah Ya ba muqamin gwamnan Kaduna. Shi kuwa sananne ne a qasar nan shi ne Razdan na Kano, ya kuma daxe a Barno. Shekarunsa dai ashirin da takwas a nan qasar yana yi mata ayyukan ci gaba. Ya saba da 'yan Arewa qwarai, ya kuma saba da Qasar nan. Saboda haka ba baqo ba ne a wannan kasa. Domin ko sa adda gwamnan Kaduna ya je hutu, Mr. Patterson aka baiwa wakilcin Nijeriya ta Arewa. A wannan lokaci sai jama'ar Arewa suka yi masa maraba tare da fatan Allah Ya taya shi riqawa, ya qara buxa masa hanyar aiki da gaskiya da siyasa, amin. A wannan lokaci ne Arewa ta yi rashin wani qasaitaccen mutum.

Rasuwar Sarkin Katsina Dikko

Sarkin Katsina Alhaji Muhamman Dikko, C.B.E, an haife shi a shekarar 1865, a zamanin Sarkin Katsina Muhamman Bello. Yana da shekaru hudu da haihuwa Muhamman Bello ya cika. Wannan Sarki shi ne wanda ya naxa Muhamman Gixaxo mahaifin Dikko, sarautar Durvi. Bayan rasuwar wannan Sarki, sai Ahmadu Rufa'i ya gaje shi. Ya yi wata takwas yana sarautar Katsina sai ya rasu. Daga Sarki Ahmadu Rufa'i sai Ibrahim xan Sarki Muhamman Bello ya hau gadon sarautar Katsina. Ya samu shekara goma sha-biyu da wata huxu yana sarauta. Daga shi sai Musa ya sami sarautar Katsina.[1] Sarkin Katsina Musa ya samu shekara biyar yana sarauta sai Allah Ya yi masa ajali. Da mutuwar Musa, sai Abubakar xan Ibrahim ya yi sarauta. Shi ne yana da Muhamman Dikko sarautar Durvi.

Dikko yaci sarautar Katsina cikin shekarar 1906 zamanin Gwamna Lugga. Ko da yake mutumin da ne, Sarki ne irin wanda ya dace da zamani. Ba qulewa, kullum yana cuxanya cikin talakawansa, babba da yaro, mace da namiji, duk sun san shi. Mutum ne kuma mai son sha'anonin motsa jiki da na shagaltar da zuciya kamar su farauta, da wasan qwallon dawaki, yadda Sarakunan Gabas da na Turai ke yi. Shi ne Sarkin yankan da ya fara hawa da sirdin Turawa, kuma shi aka fara gani da rigar ruwa.

A wajen ilimin zamani kuma ya taimaki Turawa qwarai da gaske, kamar yadda ya taimake su a kowane sha'ani. Don shi ne Sarkin da ya fara kafa

[1] Muhammadu Bello Kagara, *Sarkin Katsina, Alhaji Muhammadu Dikko* CBE, 1865-1944. Gaskiya Corporation Ltd., NNPC Edition (2006), shafi na 2-3

makarantar 'yan mata a qasarsa a Arewa. Wajen ma'amalar addini, nan ma a gaba yake. A aljihunsa ya ciro kuxi jakunkuna ya bayar aka gina masallacin Jumma'a a Katsina da siminti. Ga shi kuma da ibada da sadaka, da taimako. Wannan qasaitaccen Sarki ya rasu ran 29 ga Janairun shekarar 1944. Sarkin Zazzau M. Ja'afaru ya wallafa waqar addu'a da begen rashin wannan jigo. A wannan waqa, Sarki ja'afaru ya ce:

Sarakin Arewa, ku zo nan mu koka,
Bisa Dikko Mamman da munka rasa.

Fa Sarkin Katsina uku ga safar,
Ya rigaye mu gun Rabbu. Allah shi sa.

Shi shayad da shi, shan da babu kishi,
A bayansa, domin fa shi ya isa.

Magamin rangwame duka har gafara,
Muka roqa ga Allah shi sanya masa.

Shi yalwata kabari, shi sa masa haske,
Da alfarmarcin wanda yayyo nasa.

Shi gadad da 'ya'yansa mulki nasa,
Shi yaxa gare su da jika nasa.

Da kaine kake jin kiran mai kira,
Ka karva gareni, aya Mai isa.

Ku duk ku sani na yi kukan rashi,
Masoyimmu Allah shi yafe masa.

Fa shi ya yi hajji fa har sau biyu,
Fa ya Rabba Rahmanu, karva masa.

Da harshen talauci fa mun roqi Allah,
Rufe shi da rahamarka, don ka isa.

Fa mun cewaziri, ko yo haquri,
Ta wagga musiba ta rashi nasa.

Da durvi magaji na ce har makama,
Mu jure ga wanga rashi, ya isa.

A Xanmasani sai mu yo haquri,
A sa mana lada a domi nasa.

Ku san mutuwa za ta na ko ga kowa,
Tafarkin da kowa ka taki nasa.

Mu roqi Ta'ala shi ba mu cikawa,
Da kyawu fa, dominsa Manzo nasa.[1]

Mr. H.R. Palmer, yana xaya daga cikin manyan Turawan Arewa na farko, ya kuma zauna a Katsina. Shi ne ya gaji Baturen da Katsinawa ke kira Musta Lubiya, wanda aka ba Joji a Katsina. Shi ne ya fara kafa haraji a qasar Katsina. Ya sa a riqa biyan farin kuxi dubu biyu.[2] Duk a wannan lokaci, Mr. Palmer ya san Sarki Muhamman Dikko, farin sani. Sun saba da juna, sun san juna, sun san halin juna. Saboda haka, da wannan kasaitaccen Sarki ya rasu, Mr. Palmer bai vata lokaci ba wajen aiko da ta'aziyyarsa. Ya bayyana mana halin wannan Sarki wanda yake samfurin Sarakunan Arewa ke nan na asali, waxanda suka taka rawar gani muhimmiya a lokacinsu. duniya kuma ta yaba matuqar yabawa. Ga abin da yace:

"Mutum wanda a cikin zamansa na duniya, ya zama zakara a cikin tsararrakinsa, saboda waxansu halaye nasa, waxanda suka bambanta shi da sauran jama'a, ya kan sami babban matsayi a cikinsu. Saboda wannan, har sai ka ji sun sanya masa suna 'Gwarzo!' Ta wannan hanya, dole ne mu kira Alhaji Muhamman Dikko 'Gwarzo'. Shi ne ya sarauci Katsina daga shekarar 1907 zuwa 1944. muhamman Dikko ya isa ace masa gwarzo, namiji mai hangen nesa! Ya zo duniya, ya bar ta fiye da yadda ya iske ta.

Alhaji Muhamman Dikko namiji ne, mai tsananin hankali da hangen nesa, wanda ya san zamanin cizawa da zamanin hurawa. Waxannan halaye nasa, sun kawo wa jama'ar qasarsa farin ciki fiye da yadda aka gane, ko aka sani aka rubuta. A cikin shekarar 1904, a qasar Hausawa, inda Fulani ke iko, ba a yarda da hanyar Turawa ba, har ma ana qinsu. Amma Durvi Muhamman Dikko, (sunansa kafin ya yi Sarkin Katsina) ya gane lallai zuwan Gwamna Lugga da mutanensa, abu ne da

---

[1] GTK Ta 105 (1944) shafi na 5

[2] Muhammadu Bello Kagara, *Sarkin Katsina, Alhaji Muhammadu Dikko*, shafi na 18.

zai kawo albarka ba masifa ba. Domin a lokacin nan, zuwan Turawa ana zaton masifa ce, har mutane na roqo Allah Ya fishe su daga cikinta!

Idan muka dubi kwanakin nan, fiye da shekaru arba'in da suka wuce, abin da zai faxo mana a rai, shi ne yadda Durvi Muhamman Dikko ya gane ainihin abin da za a ce masa gaskiya, da wanda ba za a ce masa gaskiya ba. Ganewarsa ta kai dai-dai da ta gwamnati a lokacin. Wata sa'a ma har ya fi gwamnati gane abin da za a kira farar al'ada, da wadda za a kira baqar al'ada.

Na tuna, a lokacin nan, a kan yi wa soja bulala in sun yi laifi. Muhamman Dikko, shi ne ya tsaya tsayin daka, ya qi a yi irin wannan horon ga soja. Amma duk da haka suna shiri qwarai da hafsoshin soja. Ya kan zo ma ya motsa jiki tare da su wajen aikin kafa tanti.

Wata rana, wani hafsa, ya sayi dawakan Sarkin Katsina Yaro da araha qwarai, don yana matsayin iko. Da Durvi Muhamman Dikko ya ga haka, sai ya bari, sai da za shi lifi, sa'an nan shi Durvi ya saye dawakan nan daga wurin sa, ya aika wa Sarkin Katsina Yaro da su kyauta. Ya ce gaisuwa ce ya kawo wa Sarki.

A cikin lokacin nan, a shekarar 1904 zuwa 1906, sha'anin mulki a Katsina daban yake da na kowace qasa a Arewa. Abin da ya sa bambancin kuwa shi ne, samun Durvi Muhamman Dikko. Duk Turawan mulki suna sonsa, sun kuwa yarda da shi.

A cikin shekarar 1906, wata 'yar hargowa hargowa ta tashi a Sakkwato, har aka sa sojojin da ke Katsina su ja dagar yaqi. A loton aukuwar abin babu dama! Sarkin Katsina mai ci a sa'an nan, da manyan hakimansa, su Qaura da Galadima, suka zauna a shinge suna kallo. Amma shi Durvi Muhamman Dikko, ba tare da wata ba, ya shiga aiki, ya ja daga, tare da mutanensa, wajen mutum dubu shida. A lokacin nan, wannan abu da ya yi abin jaruntaka ne qwarai. Ba a daxe ba sai Durvi ya zama Sarkin Katsina. Amma kowa ya sani, Durvi ba ture wancan Sarki ya yi ba ta qulle-qulle. Sarkin Katsina ba shi da lokacin tsayawa, ya bar hidimar Sarkinsa ya shiga waxansu qulle-qulle. Wannan aiki da Durvi ya yi ya nuna halinsa da ya fitar tun shekarar 1903, shi ne sanin abin da yake dai-dai, da kuma wanda ba dai-dai ba.

Daga shekarar 1906 har shekarar 1910 mu kan sadu da Sarkin Katsina Muhamman Dikko kusan ko wace rana, don bixar shawara. Waxannan irin shawarwari, ba irin waxanda aka saba sani ba ne tsakanin Bature da Sarki. A'a, akwai abubuwa waxanda yake sanar da ni, alhali kuwa da ba dominsa ba da ban sansu ba har abada. Ya kan nuna nufinsa kan yadda ya kamata a yi mulkin Katsina. In ka ji bayanin burinsa, sai ka ga ba kamar na mutum ba ne mai son ya sami mulki don ya danne jama'a ta hanyar cuta. A'a, shi sai ka ji nasa burin kamar na wanda yake da qaunar mutanensa ne a rai.

A zamanin nan, rubu'in kuxin qasar Katsina duk na Sarki ne. gwamnati kuma a lokacin ba ta tambayi abin da a ke yi da rubu'in nan ba. Shi Sarkin Katsina

Muhamman Dikko da kansa ya zo gare ni, ya ce, shi fa ya ga kuxin nan, rubu'i da ake ba shi a haka, ba dai-dai ba ne. ya ce shi a xiba masa albashinsa kawai a daga ciki, saura kuwa a kashe gun ayyukan taimakon qasa.

Da C.L. Temple da Sir W. Wallace suka ji haka, sai suka yarda. Daga nan aka fara Baitulmali a Katsina. Baitulmalin Katsina shi ne Baitulmalin na farko a qasar Hausa. Daga baya kuma, har ya zama samfuri, abin kwaikwayo ga dukkan qasashen Afirka.

Akwai abubuwa da yawa kuma da za a iya rubutawa a kan sarautar Muhamman Dikko a qasar Katsina. Muhamman Dikko ya yi qarfi qwarai cikin sarautarsa. Amma duk da haka bai kau da ji ba ga sauran ra'ayin jama'ar qasarsa. Kullum kunnuwansa a buxe suke wajen jin ra'ayi mai biyuwa, da wanda ba shi biyuwa. Ya ciyar da abubuwa da yawa gaba a qasar Katsina.

Sau uku, tsakanin shekarar 1910 zuwa 1930, loton da ya sami labari ga wani haxari nan ya taso mini, ko ga wata wahala na za ta tsare mini gaba ga ci gaba da aikina, nan da nan sai ya aiko masinja takanas, ya taso daga wuri mai nisa, don ya zo ya gargaxe ni. Sai kuwa in ga ba domin gargaxinsa ba, da ba yadda zan san wannan haxari.

Cikin shekaru 26 da na yi a Nijeriya, na sadu da yawancin Sarakunan Nijeriya ta Arewa ta da. Na fahimci irin wahalar da suke sha a kan zancen sarauta. Da na gane haka, sai na ji tausayinsu. Na kuma gane cewa yawancinsu lallai suna da niyyar bauta wa jama'arsu a ransu, suna kuwa iyakar qoqarinsu. Amma duk cikin Sarakunan nan da na sani can da, babu wani Sarki da nake tuna kyawawan halayensa kamar mutumin da na sani tun cikin shekarar 1904, yana Durvin Katsina, shi ne Muhamman Dikko.

Marigayi Sarkin Katsina Muhammadu Dikko ya yi qarfi qwarai cikin sarauta, ya kuma nuna misalai masu yawa, wajen iya mulki tare da tafiya da zamani. A zamaninsa ya ciyar da Katsina da Arewa gaba a fannoni masu yawa. Saboda shahararsa ne maroka ke yi masa kirari da "Kwazazzabo gaba ka ci xan Gixaxo! Madas kaxan ake tarfa ka na Sada!"[1] Idan ya shigo gari sai duk gari ya xau guxa da kirari, ana cewa,"Xan Gixaxo mai nasara! Jatau haihuwar sa'ida!"[2] Mr. Palmer mashahurin Baturen Mulki ne wanda ya bada shaidar cewar yawancin Sarakunan Arewa suna da niyyar bauta wa Jama'arsu a ransu sun kuma yi iyakar qoqarinsu.

Katsina ta yi Sabon Sarki

Sarakuna da Gwamnoni sun yiwa Arewa ayyukan ci gaban da raya qasa da jin xaxin jama'ar Arewa. An samu yin ayyuka muhimmai bayan qarshen yaqin duniya na biyu. A dai-dai wannan lokaci ne Arewa ta samu wani tauraro mai

---

[1] Muhammadu Bello Kagara, *Sarkin Katsina, Alhaji Muhammadu Dikko*, shafi na 5

[2] *Ibid.* shafi na 7

haske wanda ya taimaka gaya wajen ciyar da Arewa gaba. Wannan qasaitaccen mutum shi ne Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo.

Allahu Akbar! Muhamman ya bar duniya ke nan, Allah Ya gama shi da Rahamar Ubangijinsa, amin. To, bayan da aka gama jana'iza, aka yi wa juna gaisuwa. Kowa kuma ya tafi gida ya sake amsar gaisuwa ga wannan rashi na kowa ne a Katsina da Jihar Arewa baki xaya.

Abin mamaki, rannan, da 'yan yaran gidan Sarki 'yan qanana suka fito suna kuka, sai suka yi Yamma, buu, kamar 'yan tsaki waxanda muzuru ya cinye musu uwa. Ana kallon 'yan yaran nan ba su zame ko'ina ba, sai gidan Magajin Gari, Alhaji Usman Nagoggo. Wato Allah Ya nufe su da nuna wa jama'a ke nan cewa, "yau Alhaji Usman Nagoggo kai ne uwa!"[1]

A ran 5 ga Maris xin shekarar 1944, gwamnan Nijeriya Sir Arthur Richards ya aiko waya xauke da albishirin cewa Alhaji Usman Nagogo ne Allah Ya baiwa sarautar Katsina. Tun da aka aiko da wannan albishir sai aka shiga qasaitaccen shirye-shiryen naxin sarauta a wannan birni mai tsohon tarihi.

Zaven wannan qasaitaccen mutum ya dace sosai da sabuwar Arewa da ake shirin qafawa a shirin ayyukan raya qasa da jin daxin jama'a. Alhaji Usman Nagogo mutum ne da ya dace da zamanin da ke tafe. Yabi mahaifinsa marigayi Sarkin Katsina Muhammadu Dikko sau da qafa kuma bil haqqi da gaskiya. Saboda haka ne ya zama Xan-mowar mahaifinsa. A cikin ya'yan Sarki Dikko maza biyar Usman Nagogo ne ya fi su gogewa wajen sarauta da fahimtar zamani.[2]

A lokacin da ya sami sarauta yana riqe ne da sarautar Magajin Gari wato shi ne ke da hakimcin birnin Katsina da kewaye. Kuma yana cikin Majalisar Sarki. Har-ila-yau sau haxu yana bin mahaifinsa zuwa qasar Ingila, sau biyu yana bin sa zuwa Makka da Madina wajen aikin Hajji. Saboda haka ya fi kowa dacewa da zamanin da ke tafe.

Ran 19 ga Mayun shekarar 1944 Babban Gwamna Sir Arthur Richards ya je Katsina tare da gwamnan Kaduna Mr. J.R. Patterson don ya tabbatar wa Alhaji Usman Nagogo Sarautar Katsina. Kai, ran nan an girka shagali! Ga jawabin da Gwamna Janar ya yiwa Sarki da jama'ar Katsina:

> *Sarkin Katsina Usman Nagogo, mutanenka ne suka zave ka don ka zama jagabansu, bisa al'adarku ta zaven Sarki, tun iyaye da kakanni. Ni kuma, da nake wakilin Sarkin Ingila George na shida a*

---

[1] Muhammadu Bello Kagara, *Sarkin Katsina, Alhaji Muhammadu Dikko*, shafi na 87

[2] GTK ta 116. 19 ga Yuli, 1994

nan qasar, na zo in danqa maka duk irin ikon da ake ba wanda yake wannan matsayi da ka kai.

Ka hau gado cikin halin da ya kamata mutum ya zama Sarki, amma a lokaci mai wuya qwarai. Har yanzu yaqi bai qare ba saboda haka babban abin da yake wajibi gare mu duka, shi ne mu qara himma cikin hidimomin yaqi. Ga shi yanzu, cikin rahamar Ubangiji, tafiya ta yi nisa har mun fara hango tudun nasara. Saboda haka ina so kada ku gaji da taimako, ku bada himma sosai cikin ayyukanku, har ran da Allah zai bam u nasara.

Sarkin Katsina, kana da ilimi irin na zamani, kuma saboda himmar ubanka da hango gaba ya kai ka qasashe da yawa cikin duniya, ka ga abin da ake yi. Ka san yadda wuyar wannan aiki da za ka yi yanzu take, kuma za ka iya gona hanyoyi masu yawa iri-iri na gyaruwar zaman mutanenka da ci gaba, waxanda ya kamata a fara bi tun yanzu, kafin yaqi ya qare a tasam musu sosai.

In kana so mulkinka ya tafi sosai a cikin wannan rikitaccen zamani, sai ka riqa saura-rawa kana jin shawarwari kirki wadda majalisarka, da hakimanka, da dagatan za su kawo gare ka, kai kanka kuma ka nuna halin nagarta don su gani su yi koyi, saboda haka shawarata gare ka, Sarkin Katsina, ita ce, 'kullum karvi shawarwari kirki daga majalisarka!' su kuma ina so su riqa ba ka shawara tagari ta tsakani da Allah, Hakimai da Dagatai kuma kullum kada su sa komai gaba sai taimakon talakawansu ta kowace hanya. Duka ku tuna babban aikinku, shi ne tsare lafiyar talakawa da taimakonsu da ci gaba. Da kai da hakimanka ku ne jagaban talakawa, saboda haka sai ku lura ku bi da su ta hanya fitacciya. Ku kuma talakawa, umurnina gare ku shi ne, "ku bi Sarakunanku, kuma ku riqa tunanin abin da za ku yi don taimakon junanku, ba don taimakon kanku kawai ba.

A wajen maganar shari'a kuma, kasa alqalanka su riqe gaskiya da adalci, babu nuna sanayya ko soyayya, don hankalin mutane ya kwanta da shari'ar da su ke yi.

Haqqinku ne, da kai da majalisarka, ku gabatar da kuxin harajin da talakawa suka tara, sai akan abin da zai anfane su.

Na yi murna da ganin shirin da ake yi na gyara qasar Kaita, yadda mutanen can za suji daxin zamasu qaru da lafiya. Wato ba mutanen birni kaxai za a taimaka ba. To, wannan some ne, ina fata kuwa shirye-shirye masu kama da wannan na gyara za su watsu ko'ina a cikin qasar nan a zamaninka.

Qasar Katsina ta ci gaba qwarai a zamanin ubanka, tun ba wajen sha'anin aikin magani ba. Allah kuwa ya nufa ta riqa ci gaba haka

kullum yanzu watsuwar ilimi yana cikin abubuwan da aka sa a gaba. To, Sarki, sai ka yi iya qoqarinka qasar Katsina ta ci gaba ko yaushe, cikin kowace irin harka-har ma tafi yanzu saurin ci gaba. Muna so mu ga ilimi yana bazuwa ko'ina da sauri fiye da yanzu. In babu ma'aikata masu ilimi cikin ayyukan qasashen su ba ci gaba cikin al'amura irin na wannan zamani. Ban da wannan kuma, ilimi wajibi ne a ko'ina, in dai a hannun mutanen qasar za a xanka ma'amalar taimakon mutane da ta gyara qasa da ake shiryawa, ba a hannum baqi ba. Duk wannan kuwa sai da ilimi. Don haka sai duk ku miqe, ku qara himma qwarai ilimi ya yaxu.

To, ga Sandar girma, ga takardar sarauta na danqa maka, na kuma roqi Allah Ya baka tsawon rai da lafiya. Amma ina so, babban abin da, za ka tsare a cikin zuciyarka, shi ne lura da alhakkin mutanen nan, da Allah Ya sa ka a gabansu yau. Amin.[1]

A Lokacin da gwamnan Nigeriya ya tabbatar wa Alhaji Usman Nagogo Sarautar Katsina, ya miqa masa sandar sarauta tare da kayayykin sarauta na gargajiya wanxanda suka qunshi: takubba biyu, da tambari da tukunyar qarfe.

Takobi guda, da shi Sarkin Katsina Korau ya kashe Sarkin Katsina Sanau. Sarki Korau kuwa shi ne tushen Sarakunan Have na Katsina. Har yanzu kirarin Sarkin Katsina shi ne: magajin Korau, yanqe majixi, baqon Sanau! Takobi guda kuwa, Sarkin Katsina Agwaragi ne ya qwato shi daga Sarkin Gobir Yakubu, da ya kashe shi a wani yaqi, yau fiye da shekaru metin.

Ga kuma "gwauron tambari" nan wanda Galadiman Katsina ya kan buga sau goma sha-biyu (12), ranar naxa Sabon Sarki, kuma in za a naxa Qaura, ko Durvi, ko 'Yanxaka, ko Galadima, ko Sarkin Sulluvawa, ko Dambo sai a buga shi sau uku. A zamin da, in an ga yaqi, sai a hau bisa soron Bawada da shi a buga, a sanar da gari ba lafiya.

Wannan guda kuwa tukunyar qarfe ce, tun ta Sarakunan Have. In za a fita, a cikinta Sarakunan Have ke dafa daurin taurin rai, manyan Majalisa su sha. Wai kowa ya sha jiqon nan, babu sauran tsoro a fagen fama! Ita ma har ana yiwa Sarki kirari da ita, ana cewa: "Korau, abu gunurun! Korau, mai tukunyar qarye!"[2]

Ba cikin gari aka yi taron ba, sai dai a can filin qwallon dawaki na qofar 'Yanxaka. A Kudu da filin aka yi rumfuna uku, daga Gabas kuma aka kafa alfarwa guda. Rumfa ta tsaka ita aka qawata saboda Gwamna da manyan baqi na qasa qasa. Rumfa ta Yamma kuma nan ne hakiman Daura su ke, ta Gabas kuwa

---

[1] GTK ta 116. 19 ga yuli, 1944

[2] *Ibid.*

Turawa ne da akawu-akawu da yawancin ma'aikata na Katsina. A kewayen filin duk an shirya yadda hakimai za su tsaya da mutanensu. Kowane hakimi, in ya kai mutanensa wurin da za su tsaya, sai kuma ya baro su, ya tafo ya tsaya a gaban rumfar, kamar taki talatin. Kafin dai qarfe bakwai da rabi filin nan ya cika da 'yan Adam, kowa ya yi ado fes, kamar salla.

Can sai ga gwamnan Kaduna Mr. J.R. Patterson tare da Razdan, suka zo suka zauna. Ba a daxe ba, sai ga gwana cikin mota, 'yan doka sun rako shi a kan dawaki. Hakimai suka sauko daga kan dawakinsu, suka yi gaisuwa. Razdan ya aiki Qaura, ya je ya kira Sarki. Ashe tun da daxewa Sarki ya zo, yana can cikin alfarwan nan ta daga Gabas! qasa! Nan fa kallo ya so ya bar wanda bai gani ba! Domin kuwa dawakin zage goma sha biyu ke gaban Sarki, shi kuma yana bisa wani ingarma yana takawa xai xai, 'yam bindiga sun kewaye shi. Da isowarsa sai ya sauka, ya iso cikin rumfa suka gaisa da Gwamna.

Aka yi tsit duk filin, sa'an nan Alqali ya sake bai wa Sarki rantsuwa. Yana gamawa Gwamna da Sarki suka yi tsaitsaye suna fuskantar juna. Gwamna ya ka da baki, ya yi jawabi.

Yana qarewa sai ya miqa wa Sarki duk kayan sarauta, ya kuma ba shi hannu suka gaisa. Daga nan kuma sai M. Isa Kaita ya karanta jawabin Gwamna da Hausa. Sarki ya sauka daga kan karaga, ya zauna bisa kilishi. Galadima ya zo ya sake bulbula masa rawani, ya kuma buga gwauron tambari na Katsina sau goma sha biyu.

Jawabin Sabon Sarki

"Babbar daraja ce gare ni da mutanena, da Gwamna ya tafo nan don ya naxa ni Sarki na goma na Katsina. Mun gode maka, godiya kuwa wadda ta fito daga tsatson zukatammu.

"Ku jama'ar Katsina da Sarakunanku, ku kuka zave ni, in zama shugabanku. Ina bukatar taimakonku tsintsa, wurin riqe wannan babbar amana da kuka danqa a hannuna. A cikin shekara 38 da tsofona yake cin sarautar Katsina ya yi abu da yawa, don ya inganta kyaun zamanku. Ni kuma, da ku jama'ar Katsina, yanzu mu za mu haxa kammu mu ci gaba da aikin nan da aka bari a hannummu.

"Har yanzu mulkin Sarkin Ingila suna nan suna ta faman yaqi da muggan mutanen nan, waxanda suka hana duniya zama lafiya, waxand a ba su son kowa sai kansu. Da yake muna cikin wannan babban mulki, mun yi namu yin a wurin kitala da abokan gaba. Na ji daxi qwarai da Gwamna ya yaba da qoqarin da muka yi. Ba za mu sassauta ba ko kaxan wurin taimakon yaqi, sai mu qara qoqari fiye da na da, har a samu nasara.

"Ya jama'ar Katsina, sai fa mu zage damtse mu haxa kammu, yadda za mu taimaki junammu, don mu ji daxin zama, kuma 'ya'yammu su ji. Ina roqon Allah ya taimake mu.

"Ina da Magana xaya da ku alqalan nan, Kun ji sarai abin da Gwamna ya ce yanzu, zaman lafiyar jama'ata da walwalarsu duk sun danganta ga yadda kuka riqa yanke kmusu hukunci. A kullum ku riqe yin hukunci daidai da yadda shari'a ta ce, ba sani, ba sabo, ba zave.

"Akwai abubuwa da yawa waxanda za mu yi yanzu, don gyaran zaman jama'a, haka kuma nan gaba bayan yaqi ya qare. Ku jama'a, lalle kowa ya taimaki kansa kuma ya taimaki 'yanuwansa. Lalle mu qara buxe makarantu saboda 'ya'yammu, mu qara samun abubuwa saboda kiwon lafiyar jama'a, mu qara samun abinci mai kyau mayalwaci, mu samu gidaje waxanda suka fi na yanzu. Da taimakon shawara ta gari wadda Turawa su ke ba mu kullum ba fashi, da kuma qoqarimmu (wannan qoqari namu fa shi ke gaba), duk abubuwan nan da kuma waxansu da yawa duk za mu same su, in Allah ya so.

"Ina fata, ranka ya daxe, ka isad da mubaya'ata da ta jama'ata ga Mai girma Sarkin Ingila. Kuma ka tabbatar masa mafificiyar biyayyarmu da kulawarmu ga aiki, don taimakon mulkin nan da yake shugaba. Muna alfahari da zama cikin mulkin nan.

"Na gode wa Sarkin Daura da Sarkin Argungu da wakilan Sarakuna 'yanuwana duk, waxanda suka halarci naxa ni. Allah ya taimake mu ya sa mu tafarki na gari."

Hakimai suka yi ta zuwa da xai da xai dai, suna yin mubaya'a. Sarkin Daura da Sarkin Argungu M. Isma'ila da Ciroman Kano Alhaji Muhammadu Sunusi da Wazirin Sakkwato Abbas da Iyan Zazzau, da sauran wakilan Sarakuna na qasashe, su ma suka zo suka yi hannu da Sarki. Hakimai fa suka nufi inda mutanensu su ke. Sai im Makaman Doka Yusufu ya xauka tuta daga kan dokinsa, xaya daga cikin hakimai sai ya zaburo a sukwane da jama'arsa, ya zo ya yi wa Gwamna jafi. Aka yi ta yin haka har aka kai ga 'yan Sulke. Bayan sun yi jafi, sai kuma suka jera a gaban rumfa suka yi ihu, yadda aka saba yi ga al'ada.

Shi ke nan, Gwamna da Turawa suka koma bariki, sauran jama'a kuma suka tasar ma qofar Soro. A nan kuma Sarki ya yi lima aka yi ta yi masa jafi bi da bi, kamar yadda aka yi wa Gwamna. Da aka gama, Sarki ya sallami jama'a, ya ce kowa ya koma gona ya himmantu ga noma gyaxa. Ya sa kuma aka yi shela a kasuwa, kowa ya qara gonarsa ta gyaxa.

A wannan lokaci qasar Ingila na buqatar gyaxa don taimakon yaqi. Wannan sabon Sarki bai vata lokaci ba wajen kiran Katsinawa da su himmatu su noma gyaxa.

Arewa ta yiwa Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo maraba a dai-dai lokacin da ake aiwatar da qasaitaccen shirin Raya Qasa da Jin daxin jama'a. A lokacin da ya hau kan gadon sarauta kuwa ana tafka yaqin Hitler. Shi ne Sarkin da

gwamnatin Arewa ta tura fagen wannan yaqi. Zuwansa kuma ya qwarzanta sojojinmu ya kuma gaggauta kawo qarshen yaqin a shekarar 1945. Saboda himma qwazo da gudunmawar da yake bayarwa wajen ci gaban qasar nan ne sai Mai martaba Sarauniya ta karrama shi da lambar girma.

Nagogo Ya Zama Sir

Mai martaba sarauniyar Ingila cikin karamcinta ta baiwa Sarkin Katsina Alhaji Usuman Nagogo lambar K.B.E. A dalilin haka sai ya zama Alhaji Sir Usuman Nagogo ke nan. An bayyana bada wannan lambar girmamawa ne, a sunayen da aka aiko, a lokacin shagalin tunawa da ranar haihuwar Mai martaba a shekarar 1962. Shi ne ya sami lambar girmamawa mafi daraja.

A lokacin wannan shagali ne kuma aka baiwa sauran manyan mutane Turawa da Baqar Fata lambobin girmamawa masu daraja daban-daban. An baiwa Alhaji Muhammadu Ndayako, Etsu Nupe da Mr. John Taylor lambar C.M.G. Malam Muhammadu Tukur, Sarkin Muri da Mr. Hector Gordon Jelf sun sami lambar C.B.E.

Waxanda suka sami lambar O.B.E kuwa sune: Malam Ibrahim Musa Gashash, da Mr. George Uru Ohikere, da Alhaji Umaru, Sarkin Pategi, da Mr. Arthur Frank Bryson, da John Edward Evans.

Waxanda aka baiwa lambar M.B.E sune: Alhaji Abubakar Garba, Madakin Bauci, da Alhaji Muhammadu xan Malam, Wamban Katsina, da Zanna Luntina Mustapha Laisu da Alhaji Haruna Qassim, da Mr. George Ajai Balogun, da Alhaji Alhaji Dogondaji da Alhaji Abba Annas Baba.[1]

Bayan sabon Sarkin ya sami shekaru uku a kan karagar mulki sai gwamnan Kaduna Mr. J.R Patterson ya yi ritaya, Sir Eric ya amse shi. Sir Eric ya taka rawar gani, a wajen yin ayyukan ci gaba a Arewa. Saboda yana xaya daga cikin Gwamnonin farko da suka aiwatar da gawurtaccen aikin shirin Raya Qasa da jin Daxin jama'ar Arewa. Saboda haka sai mu yi maraba da zuwansa Arewa.

Bayan Alhaji Usuman Nagogo ya samu kusan shekara uku da sarauta sai Gwamnan Kaduna Mr. J.R. Patterson ya yi ritaya. Wannan ya sa Arewa ta yi maraba da sabon Gwamna.

Maraba da Eric Thompstone

Keftin E.W Thompstone, K.B.E., C.M.G., M.C., (1947-1942) Cif Kwamishinan Lardunan Arewa, xan shekara hamsin da biyu. A Shrewsbury, ya shiga aikin soja a shekarar 1915, a lokacin yaqin duniya na xaya, inda ya yi yaqi a qasar Faransa da Italiya. Saboda qwazo da jaruntakarsa a wannan yaqi, aka ba shi

[1] N.C/No 1000, Asabar 6/2/1962

lambar jaruntaka, wato "Military Cross." Ya kuma sami lambar jaruntakar qasar Italiya da ake kira Italiyan Medal for Military Valour. Saboda haka Keftin Eric, jarumi ne na gaske.[1]

Ya nufo Nijeriya a jirgin ruwa cikin watan Yulin shekarar 1919. Da Isowarsa sai aka aiko da shi nan Arewa. A Naraguta ya fara zama, cikin qasar Jos. Ya shekara talatin da uku yana aiki a Qasar nan. Ya kuwa zauna a fiye da rabin qasashen Arewa. A lokacin da Lardin Nasarawa na nan, Sir Eric ya zauna tare da gwamnan Golkwas Sir Charles Arden – Clarke, lokacin suna Dio-Dio. A wannan zamani Kafi, da Jema'a, da Wamba da Akwanga duk suna qarqashin wannan lardi ne. Sir Eric ya zauna yana Di'o a Yawuri, da Birnin Kabi, da Sakkwato kanta. Ya sami shekara takwas yana aiki a Sakatariya ta Kaduna cikin shekarar 1947, ya zama Razdan a Adamawa, da Barno da Kano. Babu lardin da bai sha zuwa ba. Kuma babu qasar da bai san ofishin Di'o na qasar ba. Akwai sake-sake da yawa da suka auku a idon Sir Eric a Qasar nan, sa'adda ya zo, da kyar mutum zai yi tafiya wadda nisanta ya shige mil goma sha-shida a rana xaya. Yanzu ga shi mutum yana iya shiga jirgin sama ya yi tafiya mai nisan gaske a rana guda.[2]

Wannan jangwarzo ya zo Nijeriya bayan qarshen yaqin duniya na Xaya, a shekarar 1919. A shekarar 1942 ya zama Babban Razdan ya kuma sami qarin girma a shekarar 1942, a lokacin da ya zama Cif Kwamishina wato *Chief Commissioner*, yana da shekaru talatin da uku a Nijeriya. Iyayensa masun yi aiki a Arewa.

Mahaifinsa Dr. S. W. Thompstone, ya yi aiki a lardunan Arewa. A lokacin da ya zo Nijeriya, yana likita mai kula da lafiya, ya fara aiki a yankin Bakin Kogi, wato *River's Protectorate* a shekarar 1893, ya kuma zama shugaban likitocin Arewa a shekarar 1903 bayan kafa Mulkin Mallaka a Arewa kuma shekara goma da shigowarsa Nijeriya.[3]

Leftana – Gwamna Sir Eric Thompstone, dattijo ne da ya daxe yana bauta wa wannan qasa. Abin sha'awa kuma shi ne ba shi kaxai ba, har tsohonsa ma ya yiwa qasar nan aiki. Tun cikin shekarar 1893, marigayi Dr. S.W. Thompstone, C.M.G., F.R.C.S., F.R.C.P., D.P.H., ya iso Nijeriya. Ya kama aikin likita a Fatakwal, cikin Lardin Koguna a Jihar Gabas. Daga baya aka haxe wannan qasa ta zama sashen Ikko, a Nijeriya ta Kudu. Bayan shekaru sun juya, sai Likita Thompstone ya shiga cikin jama'ar gwamnatin Lugga. Ya zama shugaban likitocin Arewa. Ya riqe wannan matsayi, har zuwa lokacin da ya yi ritaya a shekarar 1911. A wannan lokaci ko gine-ginen ofisoshin hedkwata a Zungeru (Dungurun) ba a qare ba.

---

1 *The Nigerian Citizen*, 6 ga Janairu 1950.

2 GTK, 30, Ga Janairu 1952

3 *Ibid.*

Gyatumar Sir Eric ta taho daga Ingila cikin 1903. Ta iso wurin mijinta. Ita ce matar Bature wadda ta fara zama a wannan hedkwata.

Ya Samu Lambar Girma

A bikin sabuwar shekarar 1950 likkafar Cif Kwamishinan Lardunan Arewa ta yi gaba. A wannan shekara yana xaya daga cikin waxanda Sarkin Ingila ya karrama su da qarin girma, ya bashi lambar *Knight of the British Empire* (K.B.E.) wato ya zama Sir Eric ke nan. Yana xaya daga cikin waxanda suka sami wannan muhimmiyar lambar girma a Nijeriya.

A wannan lokaci ne Sarkin Ile-Ife, ya sami Lambar *Order of the British Empire* (O.B.E.). Sauran waxanda suka sami lambobi daban-daban a wannan lokaci sun haxa da Mr. T.C Hoskyns-Abrahall C.M.G., Cif Kwamishinan lardunan Jihar Yamma ya sami K.B.E.; da Mr. M Greenwood, Shugaban Jami'an gona ta Samaru, O.B.E. Sarkin Yawuri da A.G Goyer, *Superintendent* na Maxaba'ar gwamnati sun sami lambar *Member of the British Empire* (M.B.E.).

An karrama mata uku waxanda suka haxa da Miss Barbara G. Schofield, Babbar Nas a Kano da Miss Susan McKennel, waxanda suka sami lambar M.B.E., sai Mother Mary Osmond ta Calabar wadda ta sami lambar (O.B.E.). Sauran waxanda suka sami lambar girmasun haxa da Mr. C.J Pleass, Sakataren ci gaba wanda ya karvi lambar C.M.G, da Mr. A.C Hands, Daraktan Binciken Kuxi, C.B.E, da Mr. Herrinton, Jami'in kula da Ilimin Qauyuka, O.B.E., da Mr. O. Ajibade, O.B.E..

Waxanda suka sami lambar M.B.E, sun haxa da Mr. F.R Sweet, Jami'i mai Kula da harkokin ci gaba, da Mr. J.K Mzerem, B.E.M.. Sa'an nan sai Mr. Hasgan Bankaxe, da Mr. Emmanuel Akande, sai Mr. R. J. P Maclaughlan, wanda ya karvi lambar *King's Police Medal.*[1]

Sir Eric W. Thompston, shi ne Cif Kwamishina kuma gwamnan lardunan Arewa daga shekarar 1947 zuwa 1951. Ya karvi wannan muqami daga Sir John Patterson. Ya kuma riqe muqamin Leftanan Gwamna na lardunan Arewa daga shekarar 1951 – 1952. A lokacinsa ne aka aiwatar da muhimman ayyuka na tallafin kuxin qarshen yaqi don gyaran Nijeriya. Wannan Gwamna ya taka rawar gani wajen yin ayyuka masu yawa don ci gaban lardunan Arewa. A ran 4 ga Disamban shekarar 1947, Mai girma Gwamna Keftin Thomsptone ya yi jawabi ga taron Shawarwarin Kuxi na Majalisa ta Jihar Arewa inda ya yi jawabinsa na farko:

> *Wannan shi ne jawabina na farko ga Majalisun nan biyu na Jihar Arewa, na kuwa yi sa'a da zan yi shi a buxe taron farko na shawara a*

[1] *The Nigerian Citizen, Vol.1 no 71*, Friday 6 ga Janairu 1950.

kan sha'anin kuxi. Yadda zan riqa yi kowace shekara a lokacin taron shawara kan sha'anin kuxi, shi ne cikin jawabina wanda za a buga kafin a yi taro, a ba ku, zan bi cikin irin abubuwan da aka yi a shekarar da ta wuce a ko'ina a Nijeriya ta Arewa, sa'an nan in tambayeku ku duba gaba. Ina fata zan nuna muku hanyoyin da nake tsammani a kansu ne za mu bi da ci gabammu.

Wannan taro, kamar yadda na ce, shi ne taron shawara kan sha'anin kuxi, nan gaba cikin wannan jawabi zan bi maganar abin da a ke ciki na maganar kuxi na wannan jiha ta Nijeriya filla filla. A taqaice dai abin da za ku duba a yanzu, ku bi sosai sosai, shi ne abin da za a kashe a shekara mai zuwa na kuxin da wannan jiha take da su. Waxannan kuxi sun yi wajen jaka dubu ashirin (£2,000,000)...

To, ina so in tuna muku tun da wuri, waxannan kuxi, ba su ne iyakar abin da za a kashe a Nijeriya ta Arewa baxi ba. Wato su kuxin nan su ne za a kashe a kan abubawan da kuka shawarta a yi a wannan jiha. A yanzu ba ruwanku da kuxi masu yawa da En'e En'e za su kashe a kan abubuwan da Turawan mulki suka yi masu shawara, suka bishe su, ni kuma na yarda. Waxannan abubuwa na qasa qasa ne, ayyukan qasa qasa ne na ci gabansu. Ba kuma ruwanku da sha'anonin duk Nijeriya, ko kuxin da za a kashe da ya shafi duk Nijeriya. Ko da yake sun shafi Nijeriya ta Arewa, sun shafe ta ne kan yadda suka shafi duk Nijeriya, kamar su hanyar jirgi, aikin jirgin ruwa, gidan waya, ma'aikatar Geological Survey, sha'anin jiragen sama da sauransu.

Istimat xin da za mu shirya bisa shawarwarinku, ya shafi abubuwan da aka yarda na jiha ne kawai. Saboda haka shawarwari nan ta kuxi, cikinta za a saka duk ayyukan gwamnati har da albashin ma'aikatanta. Bari in fayyace muku a nan, waxannan istimat na jahohi, bayan an yi shawara a kansu a Majalisun Arewa, ba za a bi su daki-daki a sassake a Majalisar Dokoki ba. Yadda zai yiwu a sake su shi ne in Majalisar Dokoki ta ba Gwamna shawara ya yarda, cewa ya kamata a qara ko a rage kuxin da Jihar za ta samu daga kuxin Nijeriya dukanta. Wato in aka rage kuxin Jiharmu ko aka qara, abin da za mu kashe zai ragu ko ya qaru ke nan. Ban da wannan Gwamna shi kaxai zai bi cikin irin abin da za a kashe a kan ma'aikatu daban-daban. Shi kuwa, a lokacin da yake duba sha'anin, zai jinjina irin shawarwarin da za ku bayar yanzu. Shawarorin nan sun ba ku damar kai tabbatattun ra'ayinku gaban Gwamna a kan hanyoyin kashe waxannan kuxi da aka ba Jihar nan. Ina fata za ku yi matuqar amfani da wannan dama da aka ba ku.

A lokacin da kuke shawara a kan istimat kuna iya ba da shawara ku ce ko kuxin da aka ba wata ma'aikata sun yi yawa ko sun yi kaxan. Kuma kuna iya ba da shawarwari yadda ku ke tsammani zai fi kyau a sake rabo. Kuna iya ba da shawarwari a ba da kuxi ga waxansu ma'aikatu da ba su cikin istimat ba a da, a hana waxansu ko a rage na waxansu. Amma abin da ba a ce ku ba da shawara kansa ba, shi ne ku ce a qara wa Jiharku kuxi fiye da abin da aka bayar. Abin da a ke ba jiha ya danganta ga ainihin iyakacin kuxin da Nijeriya ta samu, ya kuma danganta ga kuxin da ke buqata don gabatar da aikin gwamnati, da kuma kuxin da aka ba Jahohin Yamma da na Gabas. Aikin Majalisar Dokoki ne ta ba Gwamna shawara, ko a qara ko a rage abin da za a xiba daga kuxin gwamnati aba kowace jiha. Waxansu cikinku za su tafi taron shawara na wannan majalisa, a can za su iya yin magana a kan wannan. Ina sauraren in ji duk ra'ayinku a kan abin da za a yi cikin kuxin wannan jiha, ga dubban dubban mutanen da ke qasashen Arewa. An tabbata muku cewa shawarorin da kuka bayar da zuciyarku xaya, Gwamna zai yi maraba da ita, ni ma zan yi maraba da ita, za mu kuwa duba ta da kyau.

Yanzu zan ci gaba da ba ku bayani filla-filla, fiye ma wataqila da yadda zai zama wajibi nan gaba, a kan ayyukan da gwamnati da En'e En'e suka yi wa mutanen qasar nan daga cikin kuxin da suka samu daga qasashensu, da kuma Nijeriya dukanta, da kuma kuxin da gwamnatin Ingila ta bayar cikin harajin mutanen Ingila. Ina tsammani yanzu dai mun sani sosai a cikin zukatanmu irin ayyuka da mu ke so mu yi wa mutanenmu. Amma kuxin da muke da su, su za su iya kance irin abubuwan da mu ke iya yi. Da na ce haka, ban manta irin wahalar da mu ke ciki game da qarancin qwararrun ma'aikata, da na kayayyaki iri-iri da a ke kawowa daga waxansu qasashe ba.

Duk da haka dole ne wannan jiha ta yanka riga tata dai-dai da qyallenta. Za a ba mu waxansu kuxi, sai mu kashe waxannan kuxi ta hanya mafi kyau da mu ke iya shiryawa bayan mun yi shawara sosai. A cikin shirin nan da za mu yi, kada mu manta da wahalhalun samun ma'aikata da kayayyakin aiki. Ta shirya sha'anin nan da dabara na ga za mu iya kashe kuxin yadda waxannan wahalhalu ba za su dame mu ba…

Quxi

A cikin Takardar Bayanin Istimat na Revenue da Expenditure na Jihar Arewa saboda shekara ta 1948 – 49 wanda aka aika wa kowane Wakili da kofe tare da Shirin Istimat na Farko, an nuna manyan

hanyoyi da za a bi wajen sha'anin maganar kuxi a cikin sabon shiri na kasa qasa jiha jiha.

To, a nan ga abubuwan da za a bayyana kurum:

(a) A yanzu Majalisar Jiha ba ta da wani iko bisa shari'a ta yankam ma jiha kuxin da za ta kashe: duk kuxi na aikin Jiha, da waxanda aka nuna "Na Jiha Ne" da waxanda ba a nuna ba, a Babbar Majalisar Dokoki a ke quri'ar bashe su.

(b) Har yanzu revenue na Nijeriya kuxi xaya ne, ko nan gaba kuwa ba za a ce kowace jiha ta tara revenue nata na kanta, ta keve kuxin tsiminta ko ta ta ci bashin kanta ba. In an sami qaruwar kuxi, ko in sun kasa bayan an dai-daita lissafin shekara, za a yi qoqari a shigar da qaruwan nan ko raguwar cikin abin da za a ba jiha a shekarar kuxi mai zuwa.

Ko da yake Istimat na wannan shekara ba a tsara shi a kan sabon shiri na jiha ba tun da farko, amma an iya rarraba kuxin gwargwadon yadda aka rarraba ma'aikatan gwamnati jiha jiha, aka nuna istimat na expenditure na kowacce cikin ma'aikatun nan a kowace jiha cikin shekarar 1947-48. Wannan tsarin shi aka xauka. Istimat da aka yarda. Saboda haka sai a lura wannan tsari ba cikakke ba ne, saboda haka lallai akwai wahala wajen shirya Istimat na shekarar 1948-49 yadda zai zama dai-dai, don kuwa da wannan shiri na bana za a a yi la'akari wajen shirya shi.

Amma duk da haka wannan Istimat na bana shekarar 1947-48 da aka rarraba ya ba da damar kimanta abin da za a buqata baxi, har an ga Istimat na Jihar Arewa na bana ya zama kamar £1,730,000, kuma kuxin da a ke shirin za a bayar a shekarar 1948-49 don wannan jiha £2,210,000 ne, daga ciki za a keve kamar kashi 5 cikin xari ko misalin £100,000 don wata lalurar da za ta auku, ko don ba da qarin kuxin wajen yin aiki in waxanda aka tanada a cikin Istimat sun gaza, amma fa ba aikin da a ke yinsa daga kuxin gyaran qasa da kyautata zaman mutane na shekara goma. Duk dai jimillar Istimat na Expenditure zai zama kamar £2,110,000, wato za a qara £380,000 bisa kan Istimat na bana.

A lura, wajen duba istimat na ma'aikatun gwamnati, za a ga a cikinsu aka shigar da kuxin saboda sake tsarin albashi har £110,000 ba cikin Aji 37, Tarkace, ba kamar bana. Saboda haka layin da ke nuna "qaruwa" ba nuna qara aikace-aikacen ma'aikata yake yi ba.

Bayan an xebe qarin nan na albashi da kuxin masu aiki ga yadda za a kashe abin da ya rage daga jimillan nan ta £380,000:

Aikin Gona	*£50,000*
Makaranta	*£65,000*
Aikin Likita (har da Aikin Ciwon Barci)	*£120,000*
'yan Sanda	*£30,000*
Aikin Mulkin Qasa	*£30,000*
Fidaburdi (a) Ma'aikata	*£10,000*
(b) Gyare – gyare	*£40,000*
(c) Sabbin ayyuka	*£45,000*

Kuma a tuna, wajen kimmanta kuxin aikin makaranta a Jihar Arewa, ba a haxa har da kuxin taimakon makarantun En'e ko na mishan ba, don a Istimat na Nijeriya za a ba da wannan ba a na jiha ba. Saboda haka kuxin nan £149,500 da aka nuna a Istimat don sha'anin makarantu za a qara su da £170,000 don su ba da jimilla sosai ta £320,000.

Manyan baqin abubuwa biyu a wannan sabon tsari na kuxi su ne soke rabon gwamnati na haraji, maimakonsa sai a xebi 'yan kuxi kaxan daga cikin harajin kowane mai biyan haraji, da kuma hanyar ba da taimako daga gwamnatin jiha zuwa ga En'e na cikin Jihar. Ta hanyoyin nan biyu, da kuma ta yadda za ta karvi waxansu manyan ayyuka kamar su duba masaukan baqi, manyan hanyoyi, da gonakin jarraba iri, za ta kuma biya En'e kuxin 'yan Doka masu duba garuruwan kantoma, bitulmalin En'e duka za su sami taimakon kuxi cikin shekarar 1948-49 na £270,000 fiye da 1947-48.

Baitulmalin En'e sun qaru da kuxi cikin 1946-47 har sun iya qara kuxin tsiminsu da £550,000, jimillar kuxin tsimi ta zama £3,440,000. Jimillar revenue nasu a 1946-47 £2,590,000, expenditure kuwa £2,040,000, a 1945-46 kuwa revenue nasu £2,295,000, expenditure kuwa £1,760,000. Wannan Raruwar revenue ta £300,000 galibi an same ta wajen Rarin da aka yi na harajin talakawa ne. A waxansu wurare an Rara harajin mutane, waxanda ba masu aikin albashi ba da kamar kashi goma cikin xari, qarin nan ya mai da mafi yawan kuxin haraji a kan kowa sun zama 14.1d., mafi qaranci kuma 5s.6d. Kuma qarin albashi da kuxin masu aiki shi ma ya jawo wa ma'aikata qarin haraji.

A bana jimillar revenue na Baitulmalin En'e duka £2,630,000 ce, exenditure kuma £2,760,000. Wannan ya sa tilas a xebe daga kuxin tsimi, su kuwa an yi itimat jimillarsu za ta zama £3,310,000 a Maris

xin shekarar 1948. Ko da yake waxansu ba su ga dalilin tara waxannan kuxin tsimi ba, tun a yake ga ayyukan gyaran Rasa da yawa waxanda suka kama En'e su yi, amma kada a manta ayyukan nan ba su yiwuwa sai an sami Turawa gwanaye masu yinsu. Da ce an same su kuwa waxannan kuxi da a ke gani masu yawa ba su fi qarfin ayyukan gyaran qasa a Arewa ba.

In an zo duba sha'anin kuxin En'e kuma, lallai a tuna da sabon shirin albashin ma'aikatansu wanda ake cikin daidaitawa ta hanyar Harragin, da kuma qarin kuxin leburorin En'e yadda gwamnati ta qara nata ta hanyar Shirin Miller. Ba a san iyakar qarin kuxin da hanyoyin za su kawo ba tukuna, amma En'e sun yarda su bi hanyar da gwamnati ta bi ta "Uban Aiki Nagari" gwargwadon qarfin baitulmlinsu. Kuma don su sami damar yin haka, am ba su iznin su riqa xibar kuxin tsiminsu har shekara uku in yin haka ya zama wajibi. Amman ganin taimako iri-iri da na ambata waxanda En'e za su samu, ban yi zaton da yawa cikinsu za su buqaci tava kuxin tsimin nan ba, kuma ana fata En'e za su bar kuxin nan don yin ayyukan da aka tanade su dominsu, wato na gyaran qasa da kyautata zaman mutanensu.[1]

Wannan Gwamna ya yi cikakken bayani kuma akan ofishin Babban Ma'ajin gwamnati, da na Harajin Turawa na cikin qasa, da na Tara quxin fito, da na masu duba lissafin kuxi. Ya ce a cikin ofisoshin nan huxu, ofishin Ma'ajin gwamnati ne kaxai za a kasa shi jiha jiha.

A cikin wannan jawabi Sir Thompstone ya bayyana ayyukan 'yan Majalisar Wakilai da abubuwan da ya kamata su sa ido akai sosai. Ya kuma nuna masu iyakacin ikonsu da irin ikon 'yan Malisar Dokoki da ke Ikko a cikin bayani filla-filla mai ban sha'awa. Yana yi, sai ya tavo gumzar kuxi don gyaran qasa da kyautata zaman mutane. Daga jawabi akan kuxi, sai ya juyo kan aikin gona inda ya yi nuni da cewa, "da ni da ku duka mun tabbata arziqin Arewa a yanzu da na gaba duk a gare su ya dogara." Ya kuma qara fito da arziqin gona sosai, da humihimmanci sa ba ga Nijeriya ba kaxai ba har ma da duniya baki xaya. gwamnan ya ce:

Da yake qasashen Turai da na Asia suna fama da qarancin abinci irin waxanda manomanku ke nomawa, saboda masifar bayan yaqi, wannan zai qara wa gwamnati himmar taimako wajen sha'anin noma.

---

[1] AH/GP/SA/43, Jawabin E. W Thompstone, ga Taron Shawarar Kuxi a Majalisu Na Jahar Arewa, a Disambar shekarar 1949

Na kuma tabbata zai qara wa manomanku da ku himmar noma iyakacin qoqarinku da kuma taimakon waxanda ke matse.

Yau shekara biyu ke nan da qarewa yaqi amma har yanzu mai irin na ci yana qaranci a Turai, saboda haka aikawa da gyaxa da rixi daga nan qasar yana daga cikin manyan ayyukan wannan ofis. A lokacin yaqi an gane cewa ko da yake ana iya qara yawan kayan noma ta wajen da sa farashi mai kyau, amma yin wannan kuma yana rage himmar noma abincin mutanen qasa. Ana fata manoman Arewa su ci amfanin wannan farashi mai tsoka da aka sa a kan kaya masu mai, amma kuma har wa yau su noma abinci wadatacce, kada kuma su suxe nagartar gonarsu. Don a yi maganin suxewan nan har Masu Binciken Sha'anin Gyaxa waxanda suka zo bayan Masu Binciken Sha'anin Mai sun zo, sun shawarta cewa ya kamata a taimaki manoman gyaxa da taki irin wanda a ke yi, har wa yau kuma sun ce ya kamata a riqa noma gyaxa da injin a wurare inda babu mutane da yawa.[1]

Wani abu mai baqantawa mai kuma sanya juyayi da za a yi la'akari da shi a nan, shi ne yadda arziqin gona ya lalace a Arewa yanzu. Amma wannan arziqi ne da ya taimakawa qasashen Turai a lokacin da suke cikin matsi, bayan qarshen yaqin duniya na Biyu kamar yadda wannan Gwamna ya faxa, har ya yi kuma kambun-baka da cewa, "da ni da ku duka mun tabbata arziqin Arewa a yanzu da na gaba duk a gare su (arziqin gona) ya dogara." Ya kamata a himmatu wajen bunqasa wannan arziqi mai yalwa. Daga aikin gona sai ya yi bayani akan Gama kai, inda ya ce:

Dalilan da suka sa aka kafa ma'aikatun gama kai a jiha jiha, su ne a qarfafa tara kuxi da gama kai tsakanin manoma da masu karvar albashi, ko waxansu gwanayen ma'aikata daban. Yin haka zai sa su sami amfani wanda ba za su iya samu daga kuxin kansu ba in suna xai-xai. Wannan ma'aikata qarama ce, ma'aikata kuma har yanzu kaxan ne, don haka ya zama wajibi a qayyade aikinsu. Duk da haka dai, bana jam'iyyoyin gama kai sun qaru a Jihar Arewa. A da akwai sittin ne, amma sun qaru sun kai 109. Daga cikinsu sai jam'iyyoyi shida ne kaxai ba na tanadi ba.

Jam'iyyoyin Tanadi waxanda aka kafa su da niyyar sama wa ma'aikatan gwamnati da na En'e da na kantuna masu karvar albashi hanyar ajiye kuxi don wata rana, sun qaru daga shekarar 57 zuwa 68.

---

[1] AH/GP/SA/43, Jawabin E. W Thompstone, shafi na 10

A qarshen shekarar kuxi bara jam'iyyoyin nan suna da mutane 1,875, suna kuma da ajiyar kuxi wajen jaka xari da sittin (£160,000). Galibin jam'iyoyin nan an kafa su ne tsakanin ma'aikatan En'e. An kafa waxansu jam'iyyoyin tanadi da ba da rance guda 35 a qasar Ilorin. Waxannan jam'iyyoyi su ne banki na qauyuka waxanda ke karvar kuxin ajiya kaxan kullum, su kuma ba 'yan jam'iyya rancen kuxi da ruwa gwargwado. Akwai kuma waxansu jam'iyyoyi guda biyar a wannan Jihar waxanda a ke kira Consumers' Societies. Ma'anar waxannan jam'iyyoyi, ita ce su jam'iyyoyin za su sayi kayayyaki da kuxin ajiya, sa'an nan kuma su sayar da su ga 'yan jam'iyya. Bara kuwa war haka jam'iyyoyin nan guda biyu ne kawai. Huxu daga cikinsu 'yan jam'iyyoyin tanadi na Kaduna, da na Kano, da na Zariya, da na Bida suka kafa su. Amma xaya ce kaxai daga cikinsu ta yi aiki na 'yan watanni. Waxannan jam'iyyoyi su ke sayar wa da 'yan jam'iyyoyinsu kayan abinci, kamar su garin rogo da man ja, har da waxansu kayayyakin da su ke iya samu daga cikin waxanda aka shigo da su daga qetare, amma fa kayayyakin suna da wuyar samu qwarai da gaske. Jam'iyya ta biyar kuwa Majami'ar Mishan ta Brethren a Garkixa ta kafa ta a cikin shekarar 1942 a Arewa da qasar Adamawa, domin tsakanin mutanen wannan yankin qasa da wani kanti ya fi wajen mil hamsin. Ita jam'iyyar tana aiki ne da kayayyakin da aka shigo da su daga qetare waxanda take samu daga Jos da Yola. Wannan jam'iyya ta fara shirya yadda Consumers' Societies za su sami kayayyakin da aka shigo da su daga qetare da araha, su kuma riqa samu a kai a kai, ba kamar da ba. Jam'iyya ta qarshe tana yin abincin dabbobi da jini da tokar qasusuwa, abincin shanu mai amfani qwarai, daga ragowar abubuwan da a ke samu a mahauta ta Kano. Yau fiye da shekara kaxan ke nan da wannan jam'iyya ta zama ta gama kai. Tana sayar da abubuwan da ta yi ga ma'aikatun gona da na shanu, da masu kiwon alade.

Wajibi ne kuma in yi maganar jam'iyyoyin ciniki, domin waxansu yankin qasashe irinsu su ke yi. Dalilin kafa waxannan jam'iyyoyi kuwa, shi ne wahalar samun hanyar ciniki a cikin qasa, amma ana nan ana bincika yiwuwar kafa jam'iyyoyin ciniki masu sayar da kamar shinkafa da busasshen kifi daga Gashua, barkono daga Mubi, xinkakkun fatu daga Sakkwato, doya daga Offa, da tabarmi da malfuna daga Bida. Jam'iyyar kuma tana shawara da En'e ta Katsina a kan maganar kafa jam'iyyar gama kai wadda za ta bai wa manoman Daudawa da sabon wurin da aka shirya rance, a kuma buxe masu hanyoyin ciniki waxanda su ke buqata.

A wannan dogon jawabi mai ilmantarwa, Gwamna ya yi Magana akan Aikin Daji da kuma Qasa, Ramin Ma'adinai, Aikin safiyo da Aikin Rijiyoyi. Haka kuma ya ba da bayani akan Ma'aikatar Aikin Dabbobi da yadda za a yi maganin matsalolin qarancin ma'aikata da rashin zuwan magunguna da kayan aiki da wuri. Sannan kuma ya ce an fi mai da hankali wajen samun hanyoyin hana yaxuwar manyan cuce-cucen dabbobi. A wajen ciniki kuwa Gwamna ya ce ofishin kula da sha'anin ciniki sabo ne kuma aikinsa shi ne shirya yadda za a ciyar da cinkin qasa gaba, don abubuwan ciniki su riqa kaiwa suna kawowa ba tare da wahala ba.

An'kuma raba aikin fidaburdi jiha-jiha akwai wakilan gwamnan fidaburdi da kuma mataimakinsa. A kaxan daga cikin ma'aikatar lantarki kuwa, Gwamna ya ce manufarta itace ta ba da lantarki ga wuraren da suka cika da mutane da yawa waxanda suka ci gaba, ba a raraba ta jiha-jiha ba. Haka kuma ya yi dogon jawabi akan Aikin Jirgin Ruwa, da Aikin Jirgin sama da masu Duba Yanayin sama. Ya ce a wannan shekara an yi ta tambaya a kafa gidajen waya a wurare da dama. Ko da yake an sami ma'aikatar Gidan Waya, amma duk da haka sai shekara mai zuwa za a buqaci Baqar Fata da dama waxanda za a koya masu aiki. Ana fata kuma a cikin waxanda za a xauka za a sami 'yan Arewa gwargwado.

Gwamna ya bayyana ma'aikatar Aiki Da kyautata Gyaran zaman Tsofaffin soja, wadda ba a rabata jiha-jiha ba. Wannan ma'aikata ita cewadda ke shiga tsakanin masu ba da aiki da waxanda ke yin aiki in wani hargitsi ya tashi. Ya ce har ya zuwa watan Oktoba, tsofaffin soja 28,545 a qasashen Arewa sun je an rubuta sunayensu cikin sunayen tsofaffin soja masu neman aiki, ko da yake adadin waxanda aka sallama ga ilimi sun fi 65,000. Daga cikin 28,545 da suke neman aiki an baiwa 7,656 aiki 3,489 sun koma ga gonakinsu kowasu sana'o'i daga cikin 11,000 da suka ragu waxanda ba a ba su aiki ba. An shirin a taimake su da koyon aikin gona a Kafinsoli cikin qasar Katsina.

A taqaice ya yi jawabi a duk abubuwan da gwamnatinsa da ta yi, take shirin aiwatarwa. Daga qarshe wajen aikin asibiti da na tsabta bai bar su a ba ya ba. A nan ma ya ce:

Na ga ya wajaba kuma nan gaba in yi magana kan aikin asibiti da na tsabta, waxanda a yanzu su ke qarqashin wakilin babban gwamnan asibitoci na wannan Jihar, da yake zaune Kaduna. Hanyar rarraba komai jiha 'yan watannin baya ne aka vullo da ita, za a kuwa gama shi, kuma cikakken tsari za a fara aiki da shi cikin shekarar 1948. Dukanku dai kun san irin ayyukan asibitoc na gwamnati da na

En'e da xakunan magani da sauran wuraren kiyaye lafiya. Saboda haka zan ja hankulanku ga sauran ayyukan dai da a ke yi ne na wajen ba da magani.

Xaya daga cikin abubuwan da aka fi matsuwa da son su a yanzu da kuma nan gaba wajen qara girman asibitoci da qara yawan masu aiki cikinsu, shi ne yadda za a koya wa masu aikin. A wannan shekarar an buxe wata makaranta a Kano don a sami masu ba da magani a xakin magani. An kuma buxe wata makarantar a Zariya don a koya wa almijirai aikin yadda a ke haxa magani. Samun waxanda za a sa a makarantar waxanda ke da gwargwadon ilimin da a ke buqata al'amarin ya yi wuya qwarai. Wuraren da za a koya wa mata aikin ungozoma ana nan ana shawara kansu, har ma an kusa gama shirin yadda za a gina wurin koyo xaya a Kano. Duk waxannan makarantun, da almajirai na Arewa zalla, ana yinsu da niyyar su biya buqatun Jihar Arewa.[1]

Sir Eric babban ma'aikaci ne kuma ya yiwa lardunan Arewa ayyukan ci gaba masu yawa da ba za a manta da shi ba. Ya kuma taimaka gaya wajen shimfixa aikin mulki mai kyau. A qarshen jawabinsa ya ba da kyakkyawar shawara ga 'yan Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna. Inda ya ce:

Wannan shi ne lissafin ayyukan da suka shafi qasashen Arewa; na faxe su a taqaice. Muna fata kafin qarshen shekarar 1948 da yawa cikinsu sun yiwu, musamman ina fata a lokacin an qare ginin Sabuwar Kwaleji ta Zariya. An sa tushen abubuwa da yawa, amma fa in Arewa tana so ta cim ma sauran duniya a wannan tsere na ci gaba, to ban da vata lokaci, a kuma lura lokaci fa ya kusa qurewa.

Na yi aiki da shawarwari da wani gwamnan Nijeriya na da ya bayar bisa yadda za a xauki waxannan majalisu biyu na Arewa. Shawarwari da ya bayar ita ce a nemi iyakar taimakonku wajen sha'anin mulki kowane iri da aikace-aikace da ke cikin aikin mulkin qasar nan, a ba ku damar faxin ra'ayinku bisa yadda a ke kashe kuxin haraji ko yana amfanar jama'ar qasa, kuma ko ana kashewa ta hanya mai kyau.

Yadda ku kanku kuma za ku riqa ganin abubuwan da ke hana ci gaba waxanda muke fama da su, da hanyoyin da a ke zaton in am bi za a yi maganinsu. A ba ku damar yadda za ku duba duk wani shiri da

---

[1] AH/GP/SA/43, Jawabin E. W Thompstone, ga Taron Shawarar Kuxi a Majalisu Na Jahar Arewa, a Disambar shekarar 1949 shafi na 37

gwamnati ta yi na game da qasa, ku samo kuskure, in akwai, wanda gwamnati ta kasa ganewa, kuma ku lurar da gwamnati a kan abubuwan da ya kamata a kula da su, ku kuma matsa wajen sukar duk shawara a kan wani abu, ko a kan jama'ar qasa duka, wadda ni da masu shawarata ba mu bincike ta sosai kafin mu kawo ta ba.

Wannan ita ce shawarwari da nake aiki da ita, kuma in ni da ku mun haxa qarfi mun tsare masu taruwa suna kaucewa hanyar gaskiya, da nuna so, da adalci, in dai mun iya yin wannan, to, ku tabbata jirgin zai iya tafiya sosai kan hankali kwance komai qarfin iskar da ke hurawa a bahar maliya.[1]

Sir Eric shi ne gwamnan farko da ya fara kaxa qararrawar ku tashi ku falka 'yan Arewa, ya kuma yi gargaxin cewa, "a kuma lura lokaci fa ya kusa qurewa." Ya ba da shawarwari yadda Sarakuna da Wakilai za su riqa tafiya kafaxa da kafaxa wajen 'yin ayyukan ci gaban jama'arsu. Saboda idan aka samu daidaituwa, wajen aiki da adalci, to babu shakka za a kai ga nasara. Ya kuma ba da fatawar da a riqa sa ido akan yadda ake kashe kuxaxen jama'a da abubuwan da ake masu. Har ila yau, a riqa matsa sukar duk shawara akan wani abu ko akan jama'a domin samun tantacewa.

An yi watsi da waxannan shawarwari da Sir Eric ya bayar domin kuwa Sarakuna ba su daxe a cikin siyasa ba, aka angije su domin 'yan siyasa su ci karen su ba bu babbaka. Suke da wuqa, suke da nama. Babu mai sukar abubuwansu. Saboda haka tun daga lokacin da suka daqile ayyukan Sarakuna, sai aka shiga wata siyasa shagixaxxiya ba tabbataciya ba kamar yadda ta faro. Saboda haka sai jirgin ba ya tafiya sosai kamar yadda Sir Eric ya buqata, sai 'yar qaramar iska ke hure shi akan bahar maliya. Wannan ya sa talakawa ganin tasku da mulkin garari.

Shirin nan na raya qasa da ci gaban jama'a na shekara goma ba wai shaidar takarda ba ce da ke nuna qasar Ingila ta baiwa Nijeriya tallafin kuxi, bai kuma xauki ayyuka manya ba kawai, ya haxane da abubuwa qanana waxanda za su taimaka wajen ci gaban jama'a da bunqasa arziqin wannan qasa. Duk da haka kuma ana tafiyar da wannan shiri ba daga kuxin da Ingila ta bayar ba kawai amma har da qananan basussuka da ake samu da kuma kuxaxen da ke shigowa Nijeriya. A kwai kuma ayyuka da can da kuma yanzu waxanxa ake yinsu daga kuxaxen Baitulmali na En'e. Amma idan zan nuna maku don ku gani zahiri abubuwan da aka samu nasarar yin su a watanni goma sha-biyu da suka wuce, ya kamata in nuna maku ayyukan da aka yi a lardunan Arewa, tun daga qarshen yaqi, saboda jin daxin zaman Jama'a da bunqasar tattattalin arziqi, a wannan jaddawali:

---

[1] AH/GP/SA/43, Jawabin E. W Thompstone, ga Taron Shawarar Kuxi a Majalisu Na Jahar Arewa, a Disambar shekarar 1949 shafi na . 49-50

Abubuwa	An Gina a 1949	An gina a Cikin Shekara Uku (1945-48)
Makarantun Elementare	79	156
Makarantun Midil	2	-
Cibiyoyin Horo (Social Centres)	2	7
Fadaxa Makarantu	26	56
Xakunan Shan Magani (Dispensaries)	45	77
Asibitoci	2	2
Faxaxa Asibitoci	13	8
Ofishin Hakimai Gunduma	19	29
Kotunan Yanki	17	31
Ofisoshin Hedkwata	7	13
Ofisoshi na gwamnati	6	19
Unguwar Manyan Ma'aikata	70	91
Unguwar Qananan Ma'aikata	54	103
Barikin 'yan Sanda	3	5
Barikin 'yan Doka	5	28
Barikin Gandirebobi	1	7
Gidan Waqafi	9	10
Gidan Kurkuku	6	4
Bitinariya	11	6
Ma'aikatar, Aikin Gona	5	6
Faxaxa Wuraran koyon Sana'o'i na En'e-En'e	16	14
Gadoji	37	76
Sabbin Hanyoyi	Mil 385	Mil 313
Hanyoyi Masu Kwalta	29 Mil	Mil 22
Rijiyoyi (Kwakware)	502	1,463
Rijiyoyin Burtsatse	16	21
Bunqasa Kasuwanni a Birane	37	37
Bunqasa Kasuwannin Qauyuka	59	119
Shirin Ci gaban Birane	19	17
Faxaxa Shirin Ba da Lantarki	4	12
Gidan-Waya (Post Office & Postal)	2	5
Gidejen Waya Tangaraho	2	1
Radio Diffusion Services	562	2
An Ba da Akwatuna Rediyo (Rediyon Kwabo Biyu)	1	2
Xakunan Karatu	11	53

A shekarar 1952 wannan qasaitaccen mutum wanda ya yiwa Arewa muhimman ayyuka da suka ciyar da ita gaba a lokaci mawuyacin gaske ya yi

fensho. A sabili da haka ne Arewa baki xaya ta yi masa bankwana a lokacin da ya yi ritaya zai koma gida ya huta.

Bankwana da Sir Eric

Gidan Shawara ta ga qasaitaccen taron bankwana da Sir Eric Thompstone. A wannan lokaci ne aka haxa taron Majalisun Sarakuna da Wakilai. Majalisun sun amince da sunayen Ministocin Tarayya da Gwamna ya gabatar gabansu, sun kuma amince da sunayen Ministocin Jiha da Leftana Gwamna ya gabatar. Sun kuma naxa mambobin Kwamitin da za su zavi shugabanni. Saboda haka sai Sir Eric ya sami damar bankwana da 'yan Majalisar Sarakuna da Wakilai baki xaya. Daga qarfe goma sha-xaya (11: 00am) na safe har zuwa Magariba harkoki ba su tsinke ba a *Lugard Hall*.

Da isowar Sir Eric Gidan Shawara sai duk 'yan Majalisun suka miqe a qofar shiga zauren taro. Leftana Gwamna Sir Eric, bai vata lokaci ba wajen gabatar da sunayen Ministocin da yake buqatar Majalisa ta amince. A wannan lokaci ne ya gabatar da sunayen: Sarkin Katsina Usman Nagogo, da Malam Muhammadu Ribaxu. Sai nan da nan Malam Umaru Gwandu, Akawun Majalisa ya buxe akwatin Kaxa Quri'a, ya nuna wa kowa babu komai a ciki. Daga nan ya rabawa masu zave takardar jefa quri'ar.

Da yin haka, sai 'yan Majalisar Sarakuna da Wakilai suka riqa zuwa suna kaxa quri'unsu xai-xai da xai-xai a cikin akwatin zave. Ana gama jefa quri'a, sai Mr. N. C. McClintock, Akawun Majalisar Dokoki ya xauki akwatin ya kai wa Sir Eric, wanda ya kwashe quri'un, san nan Mr. Clintock ya nuna wa masu zave babu komai a akwatin zaven. A hankali sai Mr. McClintock ya riqa kiran kowace quri'a da "Yes," "Yes," "Spoiled Paper," "Yes," da sauran su. Shi kuwa Sir Eric yana rubuta quri'a a takarda. Quri'ar "Yes," ita ce mai kyau wadda kuma ta yi dameji wato ta lalace ita ce "Spoiled Paper."

Da haka ne aka yi wannan zave, wanda ya bi tsarin doka. Aka kuma yi zave kowa na gani ido da ido. Amma da farko masu kaxa quri'a wato 'yan Majalisa basu gane yadda za su nuna alamar kaxa quri'a ta zame ba, don an sami quri'u goma sha-biyu da suka yi dameji. Amma nan da nan sai kowa ya fahimci yadda ake buqatar ya yi wajen jefa quri'arsa. Duk mambobin sun zavi sauran Ministocin uku. Shettima Kashim ya sami quri'ar ba ja daga Malam Abubakar Tafawa Valewa da kuma biyu na rashin goyon baya daga Malam Muhammadu Ribaxu.[1]

Ana gama wannan zave, sai sabon Leftana Gwamna, Sir Bryan ya shugabanci zaven da 'yan Majalisar Wakilai za su yi. A wannan lokaci sai ya fara da bayyana sunayen Ministocin Jiha da Sir Eric ya gabatarwa Majalisa, waxanda su ne; Malam Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato da Malam Bello Kano, da Malam Aliyu Makaman Bida da Walin Barno. Nan da nan sai aka shiga jefa quri'a. An

[1] NC, 24/1/1952, shafi na 8

kuma samu hamayya mai yawa a wannan lokaci. M. Bello Kano ya sami quri'u goma sha-xaya ta qin goyon baya; Makaman Bida ya sami quri'u tara ta qin goyon baya. Amma Sardauna quri'u biyu na qin goyon baya kawai ya samu. A lokacin da ake qirga quri'u ma, Malam Ahmadu Bello karanta wata takarda yake yi hankalinsa a kwance.

Ana gama zave sai Shugaba ya dakatar da taron Majalisa zuwa 9 ga Fabrairun shekarar 1952, ya kuma umarci mambobin da su riqe kujerun su. Daga nan sai Sir Eric ya shiga Majalisa don ya yi bankwana. Ya kuma ce a lokacin taro mai zuwa, ba za a yi da shi ba domin ya bar Nijeriya. Saboda ya yi amfani da damar wannan taro ne don ya cewa 'yan Majalisu sai wata rana! Ya qara da cewa shi ne Shugaban Majalisa na farko a lokacin da aka kafa ta a qarqashin tsohon Tsarin Mulki, amma yanzu an yi sabon Tsarin Mulki an kuma gabatar da shi. Ya qara da cewa abin baqin ciki shi ne barin wannan qasa musamman barin abokai masu yawan gaske!

Mr. L. H. Gobel, Sakataren gwamnati ya yabi Sir Eric don ayyukan da ya yi wa Majalisa. Ya cewannan barin qasa na sa shi ne baqin cikin kowa. A madadin Majalisa, ya miqa godiya ga wannan Leftana Gwamna da kuma fatan alheri.

Ana gama bankwana da fatan alheri ga Sir Eric, sai ya koma kan kujerar Shugaban Majalisa don ya jagoranci Majalisar Sarakuna akan batun da ya gabatar a gabanta akan Sarkin Katsina da Sarkin Zazzau da su zama mambobin Majalisar Dokoki ta Jiha, wato *Regional Executive Council*. Saboda haka ba tare da vata lokaci ba Majalisar ta amince ba ja da waxannan Ministoci su zama mambobin Majalisar Dokoki.

Sir Eric ya yiwa 'yan Majalisar taqaitaccen jawabin bankwana., Sir Abubakar ya amsa wannan jawabi da cewa: "Majalisa na baqin cikin wannan barin qasa nasa, amma kuma ta yaba masa bisa muhimman abubuwan da ya yiwa wannan jiha." Daga qarshe Leftana Gwamna ya yi musafaha da Sarakuna. An kuma dakatar da taro zuwa 25 ga Fabrairun shekarar 1952.[1] A wannan lokaci ne Arewa ta yi wa Sir Eric Thompstone adabo sai wata rana!

A lokacin ne ake gina Sabuwar Arewa bayan yaqin duniya na biyu, a lokacin qasar Ingila da abokanta, da qasashen da take reno, ke qoqarin farfaxowa daga illolin Yaqin Duniya da wahalhalun da ya kawo. A wannan mawuyacin lokaci ne Sir Eric ke shugabancin Arewa. Wato shi ne ya kafa wa Arewa kyakkyawan harsashin ci gaba wajen aiwatar da muhimman ayyukan da kowace qasa ke buqata don samun ci gaba.

Har ila yau a wannan lokaci da ake gina sabuwar Arewa, gwamnatinsa ta sha fama da suka da qorafi daga 'yan Kudu. A lokacin ne suke kuka da kururuwar cewa wai Sir Eric"ya hana su ci gaba ya kuma bar Arewa na tafiya a hankali bisa

[1] NC, 24/1/1952, shafi na 8

turbar ci gaba." A wasu sassan kuma har tawaye da rikice-rikice ke varkewa. Amma a wannan mawuyacin lokaci ne Arewa ke zaune cikin lumana da zaman lafiya. Sir Eric ya cancanci yabo saboda kawo tsaro da zaman lafiya a shekaru biyar bayan qare yaqin duniya na Biyu. Kowa ya san wannan lokaci ne na tsari da wahalhalu a qasashen duniya.

Aikin wannan qasaitaccen Gwamna, ba mai sauqi ba ne a wannan lokaci. Akwai masu qorafin cewa ana samun ci gaba cikin hanzari wasu kuma na cewa a'a ci gaban Arewa tafiyar hawainiya ne. Amma shi Sir Eric ya zavi ya tafiyar da ragamar ci gaban jiha bisa yadda ya ga ya dace da ita ne. Shi mutumne mara son Kambawa, yana kuma kaucewa masu son neman cin alfarma da neman a san su. Haka kuma yana bi sannu da masu son zaqewa kan al'amura. Shi kuma baya tsoron xaukar duk matakin da yaga shi ne ya fi cancanta, sa'an nan ya kan xauki nauyi idan al'amura sun kasance ba yadda ake so ba. Saboda halinsa na tsayawa daram kan hanyar da yaga ya dace sun sa ba zai samu yabon ayyukan da ya yi kamar yadda ya kamata ba, amma duk da haka ya shimfixa ayyukan da ba za a manta da su ba. Abu ne da ya dace sosai ya samu qarin girma zuwa Leftana Gwamna a dai-dai lokacin da ya gama aikin mulkin a dab da zai yi ritaya.[1] Kada kuma a manta mahaifinsa da mahaifiyarsa duk sun bauta wa Arewa, sun kuma sadaukar da kansu xingum wajen ci yadda ita gaba!

Za a daxe ana tunawa da ayyukan ci gaba da Sir Eric ya yiwa Arewa. Babu shakka ya taimaka gaya wajen ciyar da wannan jiha gaba. Yana cikin rukunin Turawan mulkin da suka sadaukar da rayuwarsu wajen yiwa Arewa aiki, a wani lokaci matsananci kuma mai wuyar gaske. A lokacin da ya yi ritaya, ya bar jama'ar Arewa fiye da miliyan goma sha-biyu (12,000,000) da ayyukan raya qasa da jin daxin jama'a masu yawan gaske.

Za a daxe ana tunawa da ayyukan ci gaba da Sir Eric ya yiwa Arewa. Babu shakka ya taimaka gaya wajen ciyar da wannan jiha gaba. Yana cikin rukunin Turawan mulkin da suka qi kansu suka sadaukar da rayuwarsu kacokan wajen yiwa Arewa aiki, a wani lokaci rikirkitacce matsananci kuma mai wuyar gaske. A lokacin da ya yi ritaya, ya bar jama'ar Arewa fiye da yawan mutum miliyan goma sha-biyu (12,000,000) da ayyukan raya qasa da jin daxin jama'a masu yawan gaske. Haka zalika, mahaifinsa da mahaifiyarsa duk sun bauta wa Arewa.

Leftana Gwamna Sir Eric Thompstone, K.B.E., C.M.G., M.C., ya bar Nijeriya xungum, ya koma gida ya huta. A ranar Litinin 28 ga Janairun shekarar 1952, Sir Eric ya tashi a jirgin sama zuwa Ingila. Kafin ya tashi ya yiwa jama'a jawabi a wayar iska. Yana bankwana da Arewa duka, da kuma sauran jama'ar Nijeriya baki xaya. Sir Eric ya ce, "A lokacin da na zauna a Naraguta, babu hanyar mota zuwa Yola. Babu hanya daga Zariya zuwa Sakkwato, sai a qasa. Daga Jos zuwa Yola

[1] *Ibid*., No. 178, Thursday, 24/1/1952

akan yi wajen wata guda ana tafiya. Zuwa Sakkwato daga Zariya, ya kan kai kwana goma sha-takwas. Ba wai rashin hanya kaxai ne ba, babu motocin. A wannan lokaci xakunan magani biyu ne kaxai a duk Arewa."

Wannan Leftana Gwamna mai ritaya ya ce jama'a su duba irin qasaitaccen ci gaban da aka yi ta kowace fuska ilimi sai yaxuwa yake ta yi, ga aikin gona shi ma yana qasaita. Sir Eric ya ce ga babban abu guda da ya taimaki masu shanu. Shi ne maganin cutar bushiya da aka samu. Ya ce a da, akan sami wani duk garken shanunsa sun mutu, saboda wannan ciwo. Amma yanzu babu wannan.

Da ya karkato da jawabinsa ga Sabon Tsarin Mulki. Ya ce, "Zan koma kan Sabon Tsarin Mulki, wanda aka fara aiki da shi kwanan nan. Ku ba da dukkan qoqarinku da hankalinku akan aiki da shi. Domin kuwa da haqurewarku, da dagewa, da kuma taimakon Ubangiji, qasar nan taku za ta isa ga cika burinta."[1] Daga nan ya qarasa jawabinsa da addu'ar fata na alheri, da qaruwar arziqi ga Qasar nan tamu da jama'arta. Idan aka duba wannan bayani, za a ga ayyukan da gwamnan lardunan Arewa Sir Thompstone ya yi a shekarar 1949, kawai sun kusan yin rabin ayyukan da aka yi a shekaru uku da suka gabata daga 1945 zuwa 1948. Ko shakka babu wannan mashahurin mutum ya cancanci yabo. Daga hannunsa ne Sir Bryan Sharwood Smith ya qarbi shugabancin wannan lardi mai albarka, a watan Fabrairu na shekarar 1952. Leftana Gwamna, Sir Eric na barin gado sai Sir Bryan ya hau kan karagar Mulkin Jihar Arewa. A wannan lokaci ne kuma Arewa ta yiwa wannan sabon Gwamna lale da maraba.

Maraba da Sharwood Smith

Sir Bryan Sharwood Smith Esq., CMG., ED., KBE, KCVO., Wakilin gwamnan Kaduna, shi ne magajin Sir Eric Thompstone a mulkin lardunan Arewa, daga watan Fabrairu na shekarar 1952 zuwa watan Satumban shekarar 1955. Ya zama Leftanan Gwamna, a shekarar 1951.

An ce Sarki goma zamani goma. A lokacinsa ya nuna so da qauna ga mutanen Arewa waxanda ya daxe yana mu'amula da su har ya shaqu da su sosai. Saboda himma da qwazon aiki ya sa suke masa laqabi da

Mai Wandon Qarfe, domin shi mutum ne mai karsashi da kuzari sosai, saboda tsananin aiki ba ya zama, sai ya zama kamar wandonsa da yake sanye na qarfe ne, ba na zawwati ba. Duk wanda aiki ya gamasu da Sharwood Smith ya kaxe, shi dai bai zauna ba, balle kai abokin aikinsa ka sami gindin zama. Shi ne ya sa Hausawa suka sanya masa laqabi da wannan suna, "Mai Wandon Qarfe." Shi ke riqon Arewa idan Sir Eric ya tafi lifi. Saboda haka ya sha yin jawabi ga majalisa tun kafin ya karvi mulkin wannan jiha.

---

[1] GTK, 6/2/1952, shafi na 4

Mai Wandon Qarfe, yana cikin tsarin Turawan nan da suka bautawa qasar na tsakani da Allah; bisa qa'idar ku cuxa mu, mu cuxa ku. Ba ruwansa da irin tunanin nan na gwargwadon albashi gwargwadon aiki.[1] Mai girma Bryan E. Sharwood Smith ya yi jawabi ga "Majalisar Jihar Arewa a watan Disamban shekarar 1950 a kan Gamuwar Istimat Ta Fuxu," a matsayin Wakilin Gwamna. Ya yi bayanai masu tsawo sosai, ya kuma bayyana abubuwan ci gaba da Arewa ta samu a wannan lokaci, inda ya ce:

> *Ba lardin da ba a yi aikin gini ba. Manyan ayyuka da aka qare ko ana gab da qarewa su ne: Xakin Shawara na Tunawa da Gwamna Lugga da varin farko na Sakatariya a Kaduna, da gidajen Makarantar Gona ta Samaru, da Makarantar Pharmacy (hada magunsuna) a Zariya, da Asibitin Birnin Kebbi, da Wuraren Binciken Sha'anin Ciwon Barci a Kaduna da Vom. Ana ginin qarin Asibiti a Bauci da Sokoto, da Yola, da Kafancan, da Lokoja da Offa, kuma a Kano ana ginin Wurin Koyon Aikin Nas, da gidajen Malaman Asibiti da Ma su Lura da Ma su Haihuwa da duka ake horonsu. An sami shirye-shirye na gine-ginen asibiti a Mubi da Wukari, da Makurxi da Maiduguri, da Ilorin da Haxeija da Katsina da Daura, da Wamba.*
>
> *Shirin gini mafi girma duka shi ne Makarantar Sakandare ta yara Maza a Keffi, wadda aka qare shirye-shiryenta yanzu. Wataqila 'yan kwangila za a ba aikinta. Ana da shirye-shiryen Itisi na Mata a Maiduguri da Kabba, da kuma Itisi ta maza a Okene. A yanzu an gama Itisi ta Toro, kuma ta Mubi za a gamafiye da rabinta wajen qarshen shekara.*
>
> *Sauran aikace-aikace sun haxa duk da Gidan Saukar Baqi a Ilori da Bida, da Gidan Razdan a Lokoja (wannan ma an qare shi ko) da Asibitin Haqori da Gidajen 'yan Sanda a Kano, da gine-gine a Filin Jirgin Sama na Kano saboda fasinja da 'yan Sanda, da Wurin Tare-tare (Muzuem) na Jos, da Gidan Wayan Iska na Sokoto, da Ofisoshin lantarki na Kaduna, da gine-gine don Sha'anin Lura da Jirgin Sama a filayen jirgin sama huxu, da Gidajen Turawa a dukkan Larduna, da Gidajen Qananan Ma'aikata a Larduna biyar, da gidan waya a Katsina.*
>
> *Ma su aikin rijiyoyi suna nan suna ta yi a Lardin Adamawa, da Bauci, da Barno, da Ilorin, da Kano, da Katsina, da Niger, da sokoto, da Zariya, gwanayen wannan aiki suna duba su. Bayan waxannan kuma an sanya waxanan horarrun masu aikin rijiya suna aiki a*

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe Abutar Nijeriya da Ingila*, Shafi 5.

Lardin Benue da Plateau, musamman a sabon wurin zaman Shendam. A cikin shekarar kuxi ta bara aikin da aka yi ya shafe na duk shekarun baya. An haqa rijiyoyi 629 jimillar zurfinsu qafa 47,000. Daga cikin wannan adadi rijiyoyi 558 daga Kuxin Raya Qasa da Ingila ta bayar aka haqa su. Adadin kafin wannan shekarar 491 ne. Ana tsammani za a haqa aqalla rijiyoyi 650 masu jimillar zurfi kafa 55,000 a shekarar kuxi ta bana. Galibin kayan aiki da aka yi oda a 1947-48 sun iso, yanzu babu qarancin kayan aiki. Sha'anin xaukar kaya yaci gaba, kuma zai qara cin gaba a 'yan watanni kaxan nan gaba. Taron Mahukuntan Kayan Gona sun yi odar injunan iska fiye da guda arba'in. Waxannan za a gwada su ne, za a kafa su a Lardunan da ke jere a Arewacin Jihar Arewa, waxansu kuwa a kan ramukan ruwa. Waxansu za a sa qananan injina a jikinsu dan su riqa jawo ruwa a lokacin da babu iska. Waxansu qananan injunan iska 'yan kaxan da En'En'en'e suka saya an kafe su a Lardin Katsina, da Bauci, da Sokoto, kuma a Gumel an ajiye wani famfo da dabbobi ke juya shi. Amma dai yanzu ya yi wuri a ce ga yawan tabbatar kyawon kafe-kafen nan.

An ci gaba da shirin haqa sosai. A shekarar 1949-50 an yi ramukan ruwa goma da aka yi nasara a kansu, jimillar zurfinsu qafa 3,400. Daga 1 ga Afrilu zuwa 31 ga Agustan shekarar 1950 an yi qafa 1,200 da ramukan ruwa 4 tabbatattu (biyu daga cikinsu suka bulbulo da ruwa har ya zarce baki) da a ke haqa don a samo ruwa, kuma an yi kafa 500 da ramuka 3 don a tabbata ko da kwal a kudancin Lardin Benue. Yanzu akwai kayan kamun baki da yawa kuma an sami sabbin alolin haqa guda biyu da aka shirya su don haqa qafa 1,200.

An gama aikin famfo a Minna kuma an buxe shi tun ran 1 ga Janairun shekarar 1949. Amma yanzu ya zama tilas an rage yawan ruwan da a ke sakar ma jama'a, saboda ruwan sama bai yi yawa ba a nan wajen. A Sokoto an qare rijiyar famfo da qyar, an kusa gama sa famfo, kuma ana ci gaba da aikin wuraren sayar da ruwa da kuma wurin injin na tace ruwa. A Ilori Messrs Richard Coston Limited suna ci gaba da kyau wajen ginin datsiya da aikace-aikacen famfo. A Maiduguri galibin kayan aiki ya iso kuma kafin shekara ta cika za a soma aiki. Ana sa famfo a kan ramukan ruwa a Katsina don gwada aiki da famfo, kuma irin gwada aiki da famfon nan an yi shi a Bauci a dukkan ranin bara. An sami ruwa da yawa a 'Yola da Jimeta (inda famfon ramin ruwa ya soma aiki ko), kuma ana nan ana shirin yadda za a kai wa jama'a ruwan. An gama binciken ruwa a Gusau sai dai gwada famfo ne ba a yi ba tukuna, kuma ana yin bincike-binciken fari

a Mubi da Abuja, da Biu da Gombe, Ana yin zurfafan bincike-bincike a Jos don yin ma'ajin ruwa na biyu.

Matsalar rashin abin xaukar kaya, wadda ta gaqe aiki, an yi maganinta yanzu. An yi aiki da motocin Albion masu ton 5 guda talatin a bara, kuma bayansu an qara samun guda goma sha-biyar. Gyarawar gidajen ayukkan larduna, da qara su, da kuma samun sabbin injuna saboda su sun dinga ci gaba a shekarar. A Kano gwamnati tana sa sabbin injuna a Gidan Ayukkan Makanike na En'e da aka gama kwanan nan, kuma ana shawarwari yin irin haka a sauran gidajen Ayukkan En'e. An shirya za a riqa horon yara daga En'e-En'e a gidan ayyukan jiha na Kaduna.[1]

gwamnan ya yi jawabi mai tsawo akan abubuwa masu amfani amma ba zaa samu kawo su ba. Wannan misali ne na ayyukan da Turawan mulki suka yi wa Arewa da karshen jawwabinsa ya ce:

To wannan ya kawo ni ga cikasawar jawabin nan. Na ba ku gajeren sahihin bayani na harkokin kowace Ma'aikata ta gwamnati a cikin Jihar nan a shekarar da ta wuce, kuma ina tsammani za ku yarda da ni cewa, ko da yake akwai 'yan gaqe-gaqe waxanda suka tilasta sake Shirin Raya Qasa na Shekara Goma, ammu zai iya kwanciya da ganin abubuwan nan da aka yi har zuwa yanzu. Dole ne in qarfafa cewa wannan ci gaba ba zai yiwu a same shi ba, da ba domin tsayayyen taimako daga Masu Ikon Wurare ba, da kuma buqatar jama'a da kansu bisa su kyautata zaman al'ummar da su ke zaune a cikinsu.

Wannan ita ce Gamuwar Istimat ta qarshe ta wannan Majalisa yadda aka shirya ta, mulkinta a yanzu. Bisa sabon shirin mulkin da zai zo, qarin yawan wakilai a majalisa zai qara ba jama'a damar sa baki a cikin Mulkin qasarsu, kuma igiyar Mulkin nan da aka qara masu za ta ba su damar kafa dokokin da za su shafi Jihar nan, waxanda su ke ruwan Majalisar Jihar nan ne kurum, a nan gaba. A sabon taron gaba za a sami waxansu baqin fuskoki, to amma duk da haka ina fatar cewa a qalla duk waxannan daga cikinku waxanda suka yi gudunmawa a da ga alfarmar wannan Gidan Shawara za su komo su taimaki sabbin mashawarta, su yi masu ja gora a cikin xabi'an nan ta taimakon juna wadda take ita ce harsashin da lallai ne mu xora farin cikin qasar nan da arziqinta a kanta nan gaba. Kamar yadda Lord Milverton ya tava cewa ne "Samun nasarar kowane taro

---

[1] AH/GP/SA/A7: *Jawabin Mai girma Sharwood Smith ga Majalisar Jihar Arewa*, shafi na 40-42.

na sha'anin mulki ya dangana a kan girmamawarsu ga hanyoyin gargajiya da alfarma, wato dai a kan girmamawarsu ga kawunansu.[1]

A watan Yuli na shekarar 1952, Mai girma B.E Sharwood Smith, Leftanan Gwamna na Jihar Arewa ya yi jawabi ga Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai, inda ya bayyana masu irin ayyukan ci gaban da gwamnatinsa ta kawo wa wannan jiha. A kaxan daga cikin jawabin aikace-aikacen waxansu ma'aikatun gwamnatinsa ya ba da labari a kan:

Ma'aikatar Ilimi

Lokacin da Majalisar Sarakuna ta yi taronta na qarshe na yi alqawarin cewa zan kafa Kwamitai biyu. Xaya ta Shirya Tsare-tsare na game da Yaqi da ilimin Manya, ta biyun kuma saboda bincika duka matsalolin nan na gama da addini da koya nagarta a makarantu, da wuraren koyo. To an kafa waxannan Kwamitai har sun fara aiki. Ta farko ana kiranta "Kwamitin Yaqi da Jahilci," ta kawo tsare tsare da kuma shirin aiki sosai, na game da duk fuskokin ilimin manya, za kuwa a fara wannan aiki sosai daga ran 1 ga Oktoban shekarar 1952, bayan an yi wani taron farko na waxansu turawan da ke aiki musamman, da kuma wakilan larduna, wanda za a yi a Zariya a qarshen watan Satumba. Na aika da umurnai ga duka Razdantai kan wannan magana, ciki na umurta lallai su gabatar da duka aikace-aikacen nan da ke game da Yaqi da Jahilci bisa kowane aiki, na kuwa amince cewa za mu ci nasara nan da nan cikin watannin nan goma sha-biyu masu zuwa.

Xaya kwamitin an shirya shi don "ya duba yadda ilimin nan da ake bayarwa a duka makarantu da wuraren koyo iri-iri na cikin Jihar nan za a fi maida qarfinsa ga ginin hali, da kafa qa'idodin addini a cikin zukatan 'yan makarantar nan, da samun 'yan qasa masu basira, kuma marasa son kansu, da kuma inganta son aiki a zukata 'yan makarantar nan da na wuraren koyon nan. Wannan Kwamiti ta yi taro a tsakiyar Afrilu, ta yanke shawara cewa kafin ta ba da waxannan shawarwari wajibi ne ta binciki matsalar nan duka xai xai, ta hanyar ziyartar makarantun nan da wuraren koyon nan, don ta gano irin wuyan nan da ake bayarwa a yanzu. Bayan haka an tambayi mutane da yawa, turawa da baqar fata, su ba da ra'ayinsu a kan wannan magana. Kwamitin nan za ta duba ra'ayin mutanen nan, da

[1] *Ibid*., shafi na 46

kuma abubuwan da mashawartanta suka binciko, ta ba da shawarwari hanyoin inganta irin wannan koyarwa, idan aka ga hanyoyin yanzu ba su cika wadatarwa ba.

Wurin koyar da ilimin Qauye na farko a cikin Jihar nan an buxe shi a Bauci cikin watan Yuni da ajin almajirai 22. Wannan wurin koyo zai koya wa malamai fannin tsarin aikin lafiyar qauyuka, wanda ake fata nan gaba za a kawo shi ga duka makarantun midil da na Firamare na Jihar nan.

An buga labarin jarabawar daban-daban da aka yi kwanan nan. Yara 9 a makarantar Sakandare ta Zariya sun ci jarbawar Cambridge School Cerificate, har an ba su takardun satifiket xin nan. A Jarabawar satifiket ta malanta, maza 200, da mata 24 sun ci jarbawar Elementary Certificate Examination, kuma maza 57 sun ci jarabawar Vernacular Certificate Examination, jimilla duka 281. Bayan su an umurci mutane 141 su sake xaukar waxansu fannoni, xaya ko biyu ko fiye, waxanda in suka ci su a lokaci na biyu, za a ba su satifiket xin nan. Labarin jarabawar Higher Elementary Certificate wanda almajirai fiye da 40 suka xauka a Babbar Makarantar Itisi ta Katsina, har yanzu ba ta fito ba.

Darakta na sha'anin ya damu da rashin zurfin ma tsayin aikin nan na makarantu da yawa na qaramar Firamare na Jihar nan. Yadda yawan makarantu ya qaru, yawan malaman ziyarar makarantu bai qaru, kamar haka ba. Don haka ba a cika duba makarantu sosai ko a kai-a kai yadda ya kamata ba. Muna buqatar yaran Sakandare da yawa a Jiharn nan, amma ba za mu same su yadda muke buqata ba, sai mun iya samun isassun yara na makarantun Firamare na kirki. Makarantun nan su ne harsashi na gina tsarin mmu a kai don haka saboda a iya inganta su, kuma a qarfafa su, Darakta na yana qoqarin yadda za a iya duba su sosai fiye da yanzu. Buqatar samun malami tana da wuya, har yanzu amma a waxansu larduna har yanzu yara ba su cika son, in sun bar makaranta, su kama aikin malanta ba.

Ina son in qara wani gargaxi. Makarantu ba za su iya samar mana buqatunmu cikin rana xaya, ko wata xaya, ko ma shekara xaya ba. Yadda idonmu ya buxu a yanzu, ya faro ne tun daga qarewar yaqi a 1946, kuma ba za mu fara girbin cikakken amfaninsa ba ma, sai wajen 1956. Idan muka matsa ga samun matsayi mai zurfi a Makarantunmu, da kuma aikin malamanmu, za mu yi kyakkyawan girbi, to amma girbin fa ya kan daxe kafin ya nuna.

Ma'aikatar Asibiti

Watanni shida na farko na 1952, yadda aka saba shi ne lokacin da ake shan aiki a Ma'aikatar Asibiti saboda vullowar annoba iri-iri to, an ci sa'a a wannan lokaci, har ya wuce ba tare da wata babbar annoba ba, tsakanin cutukan nan biyu da ke kashe mutane a qasar nan, su ne 'Yan- rani da Sanqarau. Adadin masu sanqarau kaxan ne fiye da yadda aka saba samu shekara da shekaru, kuma sai a qasa xaya kurum, yankin qasar Pancin da na Shendam, nan ne za a iya cewa sanqarau ya vullo. Cikin lokacin nan an sami masu sanqarau 4,762, cikinsu 707 sun mutu. Masu 'yan rani 6,762 cikinsu 1,370 sun mutu.

An ci gaba da qarin gine-gine a asibitoci da yawa a Jihar nan. An fara aiki kan sabbin Asibitocin nan na Mubi, cikin Qasar Adamawa, da Keffi, Mishan xin nan kuma na Sudan United Mission da na Roman Catholic Mission kwanan nan za su fara ginin haxaxxun asibitocin nan nasu a Nguru da Oturkpo.

Qungiyoyin masu yawon ba da maganin nan huxu da ke aiki a nan Jihar Arewa, suna nan suna ta aikin dube-duben cuta a cikin Lardunan nan da suke yawo. Sai qungiya xaya ce kurum cikinsu. Qungiyar Filato aka nemi taimakonta wajen maganin Sanqarau, amma duk sauran qungiyoyin nan suna ta yawon yin allura ne. Likitan nan na Ido wanda ke Jos ya duba wurare da yawa a Lardunan Filato da Bauci da Barno da Adamawa, don binciken cutukan ido, da dalilan da ke kawo makanta. An sami abubuwa masu amfani daga cikin binciken nan da ya yi, wanda yake shi ne na farko da aka tava yi a Jihar nan. An keve wani layi cikin Asibitin Jos inda za a riqa duba cutoci game da ido, har kafin a gama wurin aikin idon nan.[1]

Sharwood-Smith Ya Zama Sir

A ranar Sati da Yamma ne gwamnan Nijeriya Sir John Macpherson ya iso *Lugard Hall*, wajen bikin liqa wa Sharwood-Smith lambar *Knight Commander of the Most Excellent Order of the British Empire*, wato K.B.E ga Leftana Gwamna Bryan Sharwood-Smith, ya zama "Sir Bryan" ke nan. Manyan mutane da yawa suka halarci wannan qasaitaccen biki waxanda sun haxa da Ministoci da Sarakuna da 'yan Majalisar Wakilai. Lady Macpherson da Lady Sharwood-Smith sun halarci bikin.

---

[1] AH/SNP/SA/A8/ *Jawabin Mai girma Gwamna Sharwood Smith ga Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai Yuli 1952*, shafi na . 4-5

A lokacin da Babban Gwamna ya iso wajen wannan biki sai da ya duba faretin girmamawa da Sojan Bataliya ta biyar suka yi masa. Daga nan sai Sakataren Farar hula, Mr. H.R.E Browne ya karanta qasidar baiwa Leftana Gwamna wannan lambar girma. Bayan haka ne sai Gwamna Janar ya taso ya liqawa wannan qasaitaccen mutum muhimmiyar lamba, bayan sun yi masafaha.

A bisa qa'ida bayan an liqawa mutum lambar K.B.E sai mutum biyu masu wannan lambar ne za su sa shi a tsakiya suna mara ma sa baya. Amma shi Leftana Gwamna sai ya buqaci manyan Sarakunan Arewa: da Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayero, da Shehun Barno, da Sarkin Gwandu da su maraba ma sa baya a wannan ranar biki. Da aka qare biki sai Gwamna Janar da Leftana Gwamna suka karvi gaisuwa.[1]

A wannan shekarar 1953 ce kuma Sarkin Musulmi Abubakar III tare da Sarkin Gwandu Malam Yahaya suka samu lambar K.B.E ta alfarma. A shagalin bikin naxin Mai Alfarma Sarauniya ne aka raba waxannan lambobin. Sauran waxanda suka sami lambobin sun haxa da: Mr. C.R Niven da Sarkin Katsina Alhaji Usman Nagogo, sun sami lambar C.M.G.

Waxanda aka baiwa lambar O.B.E kuwa su ne: Mr. E. Jones, na Fidaburdi da Mr. D.A Pott, da Wazirin Barno, Shetima (na Alfarma), da Alhaji Aliyu Makaman Bida (na Alfarma). Haka kuma an raba Lambar Sarauniya ga Sarakuna: Sarkin Kazaure da Sarkin Koton Qarfe, Alhaji Abdu Aguye. Waxanda aka ba lambar M.B.E su ne: Mr. W.P. Gaskell, da Mr. A Olajide (ta Alfarma) da Mr. W.B.A. J Keppel da Sarkin Misau (ta Alfarma).[2]

A qarshen wannan shekara ce kuma Arewa ta yi rashin qasaitaccen Sarki kuma wani babban jigo ga qasa baki xaya.

Rasuwar Sarkin Kano Abdullahi Bayero

Sarkin Kano Alhaji Abdullahi Bayero qasaitaccen mutum ne wanda ya bada muhimmiyar gudunmawa a lokacin Ayyukan Raya Qasa a Jihar Arewa. Shi ne Sarki na hamsin da uku daga lokacin da aka kafa Kano a shekarar 999 A.D. har zuwa zamanin da ya sami sarauta, a shekarar 1926. A lokacin da mahaifinsa Sarkin Kano Abbas ya sami sarauta a shekarar 1903, sai ya naxa Abdullahi Bayero Wazirin Kano. Hawansa kan gadon sarauta ne ya karya wani tsohon canfi a kan cewa, Ciroman Kano ba ya yin sarautar Kano.[3]

A zamanin Mai Wandon Qarfe ne Sarkin Kano Abdullahi Bayaro ya rasu. Ya rasu a ran 24 ga Disamba 1953, a gidansa. Ya rasu yana da shekara saba'in da

---

1 NC, 28/5/1953 shafi na 2

2 *Ibid*., Monday, 1/11/1953

3 Muhammadu Nalado, *Kano State Jiya da Yau; A.D. 999, 1864-1968*. Jangari Cultural Organisation, Zaria, shafi na 18.

shida da haihuwa. Shi ne babban xan Sarkin Kano Muhammadu Abbas kuma jika ne ga Sarkin Kano Abdullahi Maje Karofi. Shi ne Sarki na goma a Gidan Fulanin Sulluvawa, na tara daga Gidan Ibrahim Dabo. Daga wajen Mahaifiyarsa yana daga cikin dangin Sarkin Kano Usuman ne.[1]

A wannan rana ce Arewa ta yi rashin qasaitaccen Sarki karimi kuma mai taqawa. Duk wasu aikace-aikace a birnin Kano da sauran gururuwa sai aka dakatar da su. An rufe kasuwanni duk wasu shiryen-shiryen kirsimeti da Qwarori da Turawa ke shirin yi duk suma an dakatarda su, saboda wannan babban rashi da qasa ta yi baki xaya. Arewa musamman sai ta shiga zaman makoki.

Kashegari, a ranar Kirsimeti 25 ga Disamban shekarar 1953, da misalin qarfe takwas da rabi na safe, sai Razdan na Kano Mr. A.T. Weatherhead tare da Babban Di'o Mr. Pott, da Superintendent na 'yan Sanda Mr. Ford, da Dr. Thompson likitan marigayin suka tafi gaisuwar ta'aziyya a fadar Sarkin. A wannan lokaci kuwa suka miqa takardar ta'aziyyar Leftana Gwamna Sharwood-Smith, da nuna yabo ga wannan mashahurin Sarki, wanda ya yi suna wajen tawali'u da taqawa.[2] A shekaransu ashirin da bakwai akan gadon sarauta ya yi ayyuka muhimmai da suka raya jin daxin jama'arsa

Haka kuma Razdan ya miqa umarnin Leftana Gwamna ga masu Zaven Sarki da su bi qa'idojin naxin sarauta, suna la'akari da halayen qwarai, da nagarta da gogewa wajen mulki, da sauraren koke-koken jama'a tare da karvar shawarwari. Sarkin da za su zava su tabbata ya karvu ga jama'a sosai. 'yan kwamitin zaven Sarkin su huxu ne: Madakin Kano Alhaji Shehu Ahmadu Xan Majalisar Wakilai, da Sarkin Dawaki Mai Tuta Alhaji Bello Xandago, xan Majalisar Wakilai, da Sarkin Bai na Xambatta da Makama na Wudil.[3]

Marigayi Sarki Abdullahi ya ciyar da qasar Kano gaba tun da ya hau kan gadon Sarauta. A shekarar 1928 aka gina Babban Ofis da Baitulmali a birnin Kano. A shekarar 1930 ya buxe ma'aikatar Ruwa da Lantarki waxanda aka gina akan kuxi fiye da fam dubu xari uku. A lokacinsa ne aka gina Asibitin Shahuci wanda yake mafi girma a duk faxin Afirka ta Yamma, da Makarantar Midil ta Kano da Kotun Alqali. Yana da shekara uku akan mulki aka gina Gadar Wudil a shekarar 1929.

Wannan Sarki ne ya ba da shawarar wajen da za a kafa filin jirgin sama a shekarar 1935, inda ba tare da vata lokaci ba har jiragen Imperial Airways sun buxe wannan filin jirgin sama a shekarar 1936. Wannan fili ya qara bunqasa a lokacin varkewar yaqin duniya na biyu saboda Jiragen saman Ingila *Royal Air*

---

1 NC, 31/12/1953, shafi na 2

2 *Ibid*. shafi na . 2-3

3 NC, 31/12/1953, shafi na 2

Force da na Amirka *United States Air Force* sun yi amfani da shi. A wannan lokaci kuma aka buxe tashar giden rediyo *Radio Diffusion Services* (RDS) a birnin Kano.

Kanawa Sun Sami Wayar Iska

A ran 1 ga Afrilu 1944 aka buxe sabon tsarin nan na Wayar Iska wato Wireless Radio a Kano. A wannan rana da misalin qarfe 7 na safe, Sarkin Kano Malam Abdullahi Bayaro da Razdan Commander Carrow, suka je xakin, a filin jirgin sama tsoho, nan kusa da barikin 'Yan Sanda. Da aka natsa, Razdan ya buxe wayar Iska, ya yi nasa jawabi. Da ya qare, Sarki kuma ya tashi ya ce:

"Salamu alaikum, ya jama'a, ni ne Sarkin Kano na ke gaishe ku! Kowannenku ya san samun labari, ko ba da labari, muhimmin abu ne a zamanin da, da kuma na yanzu. A da, hanyar samun labari daga ne sa ko aikawa da labari hanya guda xaya ce, watau a rubuta a takarda. To, yanzu sai mu gode wa Allah da ya bamu irin wannan dabara, wadda da taimakonta za mu iya samun labari na nesa, kuma mu sanad da mutane da ke nesa nan da nan, ba da wahala ba. Kowa zai iya jin magana kamar yadda ku ke jin muryata yanzu, ba da wani jinkiri ba. Ya kamata duk wanda Allah ya sauqaqe masa ya yi qoqari ya samu irin wannan abin jin labari a gidansa, watau wayar Iska. Ni kuma na gode wa Allah da ya nufa a zamanina aka kawo wannan abu mai amfani a Kano. Allah ya kawo mana aminci da sauri a duniya, da arziki da lafiya da tsawon rai mai amfani. Amin"[1]

Jama'a sun yi mamaki yadda kowa ke jin maganar Sarki ram, kuma huce ba wani ture-ture ko wata hayaniya wadda zata hana mutum ji. Kano ta qara ci gaba, garin ya cika da wayoyi ga ta zance ga ta lantarki, ga kuma wannan sabuwar duk sun rarratsa shi loko-loko! Kafin ka ce me! Har mutane metan da hamsin suka biya aka kai masu gidajensu. Amfanin wayar Iska suna da yawa da muhimmanci sosai.

Alalmisali, ta wayar iska in mai gida yaga dama zai riqa samun labarun Ingila tun safe har rana ta faxi, kai, har kwanciyar barci; kuma zai riqa jin maganganu da irin Turancin da ake kira Basic English. Amma da Yamma, daga qarfe huxu zuwa shida za a riqa ba da labarai da Hausa, Yarbanci da Ibo. Za a ji labarai iri iri na yaqi da na qasa qasa, kamar su gobara da sauran irinsu. A dalilin haka ne sai aka shirya cewar M. Bello xandago, wanda ke Ankara ya dawo gida ya kama wannan aiki. Da shi da M. Isa Kaita suke irin wannan aiki a Ankara a qasar Gwalkwas. Amma kafin zuwansa sai aka baiwa M. Muhammadu Malami

[1] GTK Ta 109, 12 ga Afril, 1944

xan Alqalin xambatta Kamilu riqon wannan aiki, wanda shi ma ya jima yana aikin Information Office a Ikko. [1]

Hovvasa! Kano sai qara bunqasa ta ke yi a lokacin adalin Sarki Alhaji Abdullahi Bayaro. Kano ta yi abin kanta, za'a huta zuba jama'a cikin gari su riqa shela kan komai, wayar Iska ta hutasshe su wannan. Kuma in wani babban baqo ne ya je Kano, in yana da wani jawabi da zai yiwa kanawa, ga wayar Iska na. Madalla! Kafin wannan lokaci kuwa ana amfani ne da rediyo mai akwati wanda ake haxa wa da waya daga ma'aikatar P & T inda ake watsa labarai. Shi wannan rediyo da ta sha guda rak yake watsa masu sauraronsa. To, an sami ci gaba ke nan da zuwan *Wireless Radio* a zamanin adalin Sarki.

Shi ne Sarkin Kano na farko da ya fara zuwa qasar Ingila a shekarar 1934, a lokacin ne ya tafi da marigayi da marigayi Sarkin Gwandu. Shi ne kuma Sarkin Kano na farko da ya tafi aikin Hajji a shekarar 1937. A wannan zamani ya tafi a mota tare da jama'arsa arba'in da tara waxanda ya xauki nauyin tafiyarsu. Daga nan ne ma ya kai ziyara qasashen Masar da Falasxinu, inda ya sadu da marigayi Ibn Saud Sarkin Makka, da marigayi Yarima Muhammad Ali na qasar Masar, da Muhutin Qudus wato Jerusalem.

Alhaji Abdullahi Bayaro, Allah Ya yi shi mutum ne mai son addini ne sosai da kuma sha'awar gine-gine. Saboda haka ne ma ya gina qasaitaccen Masallacin Juma'a a birnin Kano wanda aka gama gininsa a shekarar 1951. A wannan shekara ce ya sake komawa aikin Hajj, amma ta jirgin sama.

Sarki ne masani sosai wanda yake da zurfin ilimin Addinin musulunci tare da taqawa. Saboda ya taimaka gaya wajen havaka ilimi ta buxe Makarantu da gina masallatai. Ya kuma taimaka wajen havakar da ilimin boko a qasarsa. Sarki ne da ke tafiya da zamani. Mulkinsa ya ciyar da qasarsa gaba ainun ta fannoni dabam daban.

Wannan Sarki mutum ne sahihi mai son jama'a ga shi kuma da qwazo da kuzari ya kuma sadaukar da kansa kacokan wajen ayyukan ci gaban jama'arsa. A dalilin haka ne ya samu lambar C.B.E a shekarar 1934. Ya kuma sami lambar C.M.G a shekarar 1946. [2]

Leftana Gwamna Sharwood-Smith ya daxe da sanin wannan Sarki ya kuma fahimce shi sosai, saboda haka ne ma ya ce:-

> *In mutum ya dubi rikice-rikicen da ke tafiya a Kano a lokacin, sai ya gane cewa abin da ya sanya zaman lafiya a garin shi ne samun Sarki irin Abdullahi Bayaro. Ga shi dai ya tsufa, amma irin hikimar mulki, da wayon tafiyar da da shi, sai wanda ya zauna tare da shi zai*

---

[1] *Ibid.*

[2] NC, 31/12/1953, shafi na 2

iya fahimtarsa. Ga shi dai da ilimi mai zurfi na Muhammadiyya. Ba abin yake vata masa rai kamar yadda ake ganin halin yaran zamani na lalacewa.Yara ba su girmama manyansu. Ba abin da suka sa gaba sai su sami kuxi su sheqe ayarsu. Kowane mako, sai ya fito Qofar Kudu, ya zauna filin Allah. Mace ko namiji mai kuka, ko qara, ya taho gare shi kai tsaye. Bawan Allah! Ga shi a fili yana qoqarin taimakon jama'a, amma a yadda muka sami rahoto, an cewai yana tashi sai fadawa su jujjuye duk maganar da aka yi don a basu rashawa.

Abin tausayi, in an gaya wa Abdullahi Bayaro haka shi ba shi yarda. Shi a ransa ya amince da cewar waxannan da ya ba amana haka, ba za su ci amanarsa ba. To ga shi ya tsufa, kuma jama'a na sonsa qwarai, har ma duk wani laifi da zaka zata na sa ne, ba za a gaya maka ba. Jama'arsa su basu ganinsa da wani xigo na laifi. Mu kuma Turawan Mulki ga labarai barkatai sun cika mana kunnuwa. Amma duk da haka, muna ganin duk wani babban gyara da za a ce a kawo a cikin mulkinsa, ya kamata a yi masa mutunci, a yi masa kara, a dakata da gyaran sai bayan ransa. Da ma duk abin zargi wanda jama'a suka ga ya auku, sai su ce laifin Ciroma ne, babban xansa, mowarsa. Amma duk abin da zaka ji ance maka laifin Ciroma ne in ka lalaba sai ka kasa samun abin kamawa da qarfi har yadda mutum zai yi wani abu wanda kowa zai gani.

Ana nan dai, ina qara jimawa a Kano, in qara gane cewa komaine ne za a ce da, Ciroma shi ne ginshiqin mulkin En'e ta Kano a lokacin. Haqiqa da mutum ya gama ido da Ciroma, sai ya ga yana tare da basarake, Sarkin yanka, ba ma'aikaci ba. Amma kuma can qarqashin zuciyarsa, komai ka zata gare shi, zaka iske shi mutum ne haziqi irin na aje abada labari. Ga shi ba ya da kasala. Abin da ya dage kansa, har ya fahinta cewa a ganinsa shi ne gaskiya, to ya dage ke nan. Amma in har ka samu ya yarda da kai, ya ba ka amana, shi ke nan ka samu aminin zaman duniya. Ya yi aiki mai yawan gaske wurin qoqarin tabbatar da majalisun Hakimai. Hasali ma dai, komai kaji ana faxi a bayansa, in ka gan shi cikin jama'arsa, sai ka gan shi xan Sarki ne abin so. [1]

Za a daxe ana tuna wannan qasaitaccen Sarki wanda ya zama abin koyi ga Sarakunan Arewa. Allah Ya ji qansa, amin. Tun kafin Sarki ya rasu, Mai Wandon Qarfe da Razdan Mr. A.T Weatherhead suka fara tuntuvar Ciroman Kano Alhaji Muhammadu Sunusi saboda ganin cewa in Sarkin ya rasu, ba shakka masu zaven

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe* shafi na .54-55

Sarki, Ciroma za su zava. Tun a lokacin ne Leftana Gwamna ya fara magana akan wannan abu. Ga abin da ya ce:-

> *Tun a lokacin na ga ya kamata in fara magana da Ciroma a kan wannan abin da nike zato yana tafe. Na ga tun da fari ya kamata in yi qoqari, in fitar da shi daga cikin irin ladabin nan na al'ada, in sami sanin ainihin abin da ke qarqashin zuciyarsa.*
>
> *Ran nan da shi Ciroma ya zo bariki waje na, kan wata shawara, sai na ja shi muka shiga yawo cikin lambun gidana, kamar muna duba furanni. Na ce masa Ciroma, tsohonka ba yaro ba ne ya tsufa. Ina fata Allah Ya tsawaita mana ransa. Amma komai sonmu, wannan al'amari a hannun Allah Yake. Ba abin mamaki bane, mu wayi gari wata rana mu samu kammu cikin rikicin zaven sabon Sarki. Zaven Sarki ka sani ba aikina bane. Ka sani aikin masu zaven Sarki ne na gargajiya. Ya yiwu su zave ka. Mafi qarfin zatona ma kai za su zava. Ko da shi ke wannan magana tawa zato ne kawai nake yi. Amma wannan abin da zan faxi nan yanzu shi ba bisa zato ba ne, tabbace ne: Ga shi kana da abokan gaba da yawa a wannan Birni saboda haka ka sani cewa wajibi ne ka shiga qoqarin aikata abubuwan da za su sa ka karvu ga talakawan wannan Birni. Saboda haka wajibi ne ka yi xamara ka shiga himmar sauraren koke-kokensu, da share musu hawaye. In ba ka yi haka ba, randa aka zave ka Sarki, za ka gamu da tawaye a wannan Birni. Za a yi ta jefe jefe da duwatsu, jini zai gudana, har abubuwan da ba mu zato za su auku, yadda ko an kai sunan ka ga Gwamna, ba zai karvi zaven ba.*
>
> *Ina wannan magana, ina lura da idanunasa shi Ciroma, sai na ga suna sauyawa, alamar ya ji magana mai tada hankali. Da ni da shi muka yi tsit, muna zullumi. Can sai shi Ciroma ya ce mani kana da gaskiya, kuma ka sani zan riqe abin nan da ka gaya mini ko da yaushe. Daga ran nan muka buxa wani sabon faifai na abota da wannan mutum, wanda Allah Ya nufa a gaba zai zama Sarki, kuma gawurtaccen Sarki a wannan qasa ta Nijeriya ta Arewa.*[1]

Malama Abdullahi Bayaro Sarki ne da yake son kowa ya sami ilimi wajen shekarar 1928, sa'adda ya zo Makarantar Shahuci ya fahimci babu yara daga mutanen bakin kasuwa, attajirai, sai 'ya'yan mutanen Fada kawai. Saboda haka, ya yi magana da Alhasaan Xantata da kuma wasu Tajirai a kan me yasa ba su kawo 'ya'yansu makaranta ba? Sai suka ce su na tsoron cunxanya 'ya'yansu da 'ya'yan

[1] Abubakar Imam, *Auren Zobe* shafi na . 60-61

Sarki don kada 'ya'yan saraki su riqa dukan su. Sai ya ce, to, idan haka ne, za a yi muku makaranta daga can wajen gidajenku don ku riqa kai 'ya'yanku. Sai aka gina makarantar Dala a Gabas da Dala kaxan.[1] Alhaji Muhammadu Sunusi, babban xan marigayi Sarki Abdullahi ne aka zava ya zama sabon Sarki. An zave shi ba da wata hamayya ba, a lokacin yana Ciroman Kano.

Maraba da Sarkin Kano Sunusi

Alhaji Muhammadu Sunusi shi Allah Ya zava ya zama Sarkin Kano na goma sha-xaya cikin Sarakunan Fulani a Kano. Ranar Jumma'a 25 ga Disamban shekarar 1953 aka zavi Alhaji Muhammadu Sanusi ya zama Sarkin Kano. Kashegari Sarki ya yi wa jama'arsa na Kano jawabi a cikin wayar iska. Ya bayyana musu godiyarsa, ya kuma ba su labarin irin canje-canjen da za a yi nan gaba kaxan. Ga cikakken jawabin Sarki:

> *Jama'ar Kano na gaishe ku babba da yaro. Jiya masu zaven Sarki na gargajiya sun zave ni in gaji ubana, marigayi Alhaji Abdullahi Bayero, Allah Ya ji qansa, na zama Sarkin Kano. Yau Mai girma Leftana Gwamna ya tabbatar mini da sarautar Kano. Aiki ne mai nauyi, wanda na xauka. Aiki irin wanda idan har zan iya yinsa, sai lallai da cikakken taimakonku, da amincewarku, a wannan zamani mai wahalce-wahalce, mai canje-canje da sauri da sauri. Saboda haka ne da maraicen yau nake yi muku magana ta farko a muqamin Sarkin Kano.*
>
> *An sha jin soke-soke a kan sha'anin aikin Sarautar Kano, ana cewa ya cika zama a hannu xaya, kuma ya cika zama a hanya ta tsohon mulki, da yawansa a cikin hannun qabila guda. Na xauki cikakken alqawari da zuciya xaya gareku, ku mutanen Kano, lallai zan dinga shawartar majalisata a kan dukkan al'amura, kuma zan yarda da dukkan shawara da ra'ayi na gaskiya da suka ba ni. Ina da tsananin buri, da taimakon Ubangiji, im maida haqqin jama'a ya fi komai a raina. Don in tabbatar da wannan, har na yi shawara da majalisata, kuma har na ma qudure in yi waxansu gyare-gyare:*
>
> ***Na farko**: shari'a, su malaman da su ke cikin majalisar shari'a ta Sarki ta yanzu, dukansu, ban da liman kaxai, za a hutad da su. Kuma zan sanya waxansu malamai masu ilimi, masu hali nagari, waxanda su majalisa da duk sauran jama'ar Kano suka yarda da su. Duk shari'a ta gabana za a yi ta a fili, ba cikin gidana ba, a dai wani gini*

[1] Muhammadu Nalado, *Kano State Jiya da Yau*, shafi na 20

a waje, kafin a gina mini xakin shari'a. Kuma zan tabbata a gabana ba a yi wata shari'a ba, sai kawai a kan abubuwan da shari'ar gabana take da iznin yin shari'a a kansu.

***Na biyu**: Aikin wazirai masu gudanar da al'amura. Don tsananin nufin saka majalisata ta zama ta wakilci jama'a duka sosai, na qudure har abada ba zan naxa wani xan'uwana na kusa da ni ya duba aikin shari'a ba, wato kamar Wali, ko wanda zai duba sha'anin Birni, ko wanda zai duba sha'anin Hakimai.*

***Na uku**: Sha'anin gidaje da fili da filoti: Zan sa a duba yadda shari'ar waxannan take, abin da yake wajibi a sake, kuma a rubuta ta a kuma sanad da jama'a duka.*

Kuma zan sa a gina ofis mai kula da sha'anin gidaje da fili da filoti. Haka kuma ta nan za a riqa ba da su, kuma lallai a rubuta.

Kuma wajen sha'anin kaina, wanda yake ni ya shafa kawai, na sanya majalisata su duba duk waxanda su ke cikin gidan Sarki a yanzu, kuma su yi shawara akan waxanda Baitulmali za ta baiwa 'yan kuxin abinci da kuma waxanda su ke sun yi dai-dai da in xauke su, da kuma waxanda su ke lallai a fitad da su.

Akwai kuma waxansu abubuwa na aikin sarauta, waxanda su ma suke so a duba su, kuma lallai zam maida hankalina garesu ba da jin ba. Amma lallai waxannan abubuwa da na riga na gaya muku, su ne wajibai na farko, wajen kyautata aikin sarauta cikin wannan zamani da mu ke ciki.

A cikin wannan zamani a Kano, an ga mai qasaita ce nan gaba. Yawan mutanen da ke cikinta, da girmanta, wajen sha'anin ciniki, da sana'o'i, da za su taso nan gaba, duk sun sa ta zama farda, da yadda aikin sarauta a cikinta zai shafi dukkan Nijeriya ba Jihar Arewa kaxai ba. Na qudure a raina in ga muqamin nan nata bai kasa ba.

Ina roqon Ubangiji Ya ba ni hikima da iko, yadda zan yi abin da yake so kuma aikin da zan yi wa jama'ata ya zama abin samun lada ne daga gare shi, kamar yadda yake a cikin Addininmu.

Allah Ya taimake mu, ya ba mu lafiya ya kyautata arziqimmu baki xaya, ya kuma kiyaye mu daga fitinu, amin.

Saboda haka ba tare da vata lokaci ba har sabon Sarkin Kano ya fara cika alqawarinsa na gyara majalisarsa. Waxanda aka fitar daga cikin Majalisar Sarkin Kano, su ne M. Xan'amu, Alhaji Abubakar, Alhaji Nasiru da M. Mahmudu.

Sabbin malaman da aka zava su shiga majalisar kuma, su ne M. Nuhu Limamin Yola, xam M. Musxafa. Alhaji Mamudu xam M. Zubairu Limamin

Galadanci. M. Musxafa xam M. Muhammadu Alqaliin Gwaram. Sauran cikon na huxu ba mu ji sunansa ba tukuna.[1] Sabon Sarkin ya yi kira ga Jama'arsa:

> *"Kafin in gama magana, ina so in sanar da ku cewa bisa al'ada, waxansu ashararai su kan riqa yi wa 'ya'yan sarauta habaici da baqaqen maganganu, saboda ganin ba su sami sarauta ba. Wannan ba shi da kyau. Ni da su asalimmu xaya ne. Wanda ya yi da su, ya vata mini ke nan. Waxanda suka saba yin irin wannan, su daina. Su tuna, sarauta ta Allah ce, shi ya kan ba wanda ya ga dama."*

Wannan muhimmiyar magana, wadda ta yi wa jama'ar Kano duka daxi a rai, da ita Sarki ya cika jawabinsa ga jama'arsa, kafin ya shiga gidan sarautar Kano. Jama'a sun ji daxinta, har dubbai suna cewa ya kyautu sabon Sarki ya yi yaqi da ashararan maroqa, da ashararan mararaka, da sauran ashararai, masu qulla wa jama'a sharri, Sarkin Kano yaci gaba da cewa:

> *Bayan haka ina godiya ga Allah wanda ya ba mu ikon taro a wannan wuri mai albarka. Wurin da ya kan sa ni baqin ciki in na tuna da tsohona, Marigayi Sarki Abdullahi Bayero, mai kyawawan halaye. Dukanku kun sani shi mutum ne mai tsoron Allah, mai kiwon mutunci, mai son ilimi da malamai, mai gyara qasa. Ya kan gabatar da buqatar qasa bisa buqatar kansa. Ga shi an rasa shi. Na sami wayoyin ta'aziyya, waxansu daga Nijeriya, waxansu daga waje. An turo mutane da yawa saboda ta'aziyya. Wannan duka yana nuna mana irin kyawawan halayensa ne. A wannan wuri ina godiya ga dukkan wanda ya yi mini ta'aziyya ko da takarda kowaya ko ya zo da kansa.*
>
> *Yanzu kuma da yake na sami sarauta, ina fatar wannan ya zama dalilin kwaikwayonsa. Zan yi qoqari in Allah Ya so tare da samun taimako daga gare ku har in yi fiye da haka.*
>
> *Na duba na ga a wurin nan da Hakimai da Alqalai da Muhutai da 'yan Kasuwa da masu Sana'a da Manoma da sauran ma'aikata. To, ga maganata da zan yi muku.*
>
> ***Ta xaya**: Ku Wazirai da Hakimai ku tuna da ni'imar da Allah Ya ba ku game da waxannan manyan ayyuka, ku gode masa, wato ku wahalar da kanku saboda talakawa su huta. Ku nuna adalci ga mutane, ku ji qararra-kinsu, ku nemi sanin halayen da su ke ciki, da ci gabansu, ku gyara halayen 'ya'yansu, a kwaxaitad da su shiga*

[1] GTK, 6/1/1954 shafi na 5

makaranta, a kula da dabbobinsu da makiyaya da gonakinsu, a taimake su ta kowane hali.

***Ta biyu**: Ku Alqalai da Muhutai ku tuna da umurnin Allah a kan hukunci da adalci, kar ku zalunci talake don nemar taimakon mawadaci. Ku dai-daita tsakanin mutane. Ku tuna masu zuwa shari'a suna da waxansu abubuwa da su ke son yinsu. Rashin yanke shari'a da wuri ya kan cuce su. Yawan-cinsu daga nesa su ke. Rashin kula da shari'a ya kan cuce su, ya kuma vata musu. Sai ku yi adalci ku gaggauta shari'a ko da yake wannan zai qara muku wahala da rashin sukuni.*

***Ta uku**: Ku kuma 'yan Kasuwa da ku qasa ta dogara a kan harkar dukiya, kun sani mulki sai da dukiya yake tabbata. Ku neme ta ta hanyoyi nagari. Ku nisanci cutar jama'a. Allah Ya kan sa albarka cikin dukiya ta halaliya. Ku kwaikwayi baqi wajen hanyar ciniki, ku bi sabbin hanyoyin ciniki.*

***Ta hudu**: Masu sana'o'i, abin da zan gaya muku, shi ne na ga qasashe da dama kamar Ingila da Masar da qasar Kwara da Hijez da Sudan, amma ban ga irin sana'arku a cikinsu ba, kamar saqa da jimar fata da rini da sauransu. Ku ci gaba da yinsu, ku qara kyautata su.*

***Magana ta biyar**: Ku manoma da ku aka dogara wajen abinci da dukiya. Kamar dawa, gero, shinkafa don ci a ke shuka su. Gyaxa da auduga da sauransu saboda samun dukiya. Gyaxar qasar nan sananniya ce a duniya, saboda kyaunta da tsabta tata. Ina so ku kula da noman ta da yawa. Zan taimake ku matuqan taimako. Wasalamun."*[1]

Sarkin Kano Alhaji Muhammadu Sunusi ya samu kyakkyawar horo da tarbiyya daga wajen mahaifinsa, ya kuma goge sosai wajen hulxa da jama'a da yin ayyukan ci gaban qasa. Saboda haka ba wanda ya yi mamakin ganin yadda likkafarsa ta riqa gaba cikin hanzari.

Sunusi ya Zama Sir

Kimanin mutane dubu talatin ne daga ko'ina cikin Jihar nan suka halarci taron shagalin baiwa Mai girma Sarkin Kano, Alhaji Muhammadu Sunusi Lambar K.B.E., a Kano a watan Satumban shekarar 1958. da wannanbqarin girma ne ya zama Sir Muhammadu Sunusi. Allahu Akbar! Kano tumbin giwa. Babu shakka Kano ta cancanci wannan kirari, kuma ta dace da ta yi alfahari da kanta a Arewa

[1] GTK, 6/1/1954 shafi na 6

da kuma Nijeriya baki xaya. Duk wanda ya halarci wannan biki, ya ga kuma yadda aka tsara komai cikin natsuwa da xaukaka, babu shakka zai yarda da haka. Wannan qasaitaccen biki da aka yi ba shi da wani kwatanci a wannan jiha im ban da taron zuwan sarauniya a Kaduna. An yi bikin da za a daxe ba manta da shi ba a Kano ko kuma a Jihar Arewa baki xaya.

Abin sha'awa daga cikin bikin nan shi ne Sarkin Musulmi Sir Abubakar da ya halarci bikin, an ce rabonsa da Kano shekaru goma sha-shida ke nan. Firayim Minista bai sami zuwa ba, amma Alhaji Muhammadu Ribaxu ya wakilce shi. Sarkin Gwandu Alhaji Haruna Rashid ya halarci wannan biki. Cikin manyan mutane kuma ga Cif Jojin Sudan wanda gwamnatin Jiha ta gayyato shi domin binciken al'amuran shari'a a wannan Jiha da kuma Wakilin Amirka a Nijeriya.

Bayan an kimtsa, duk manyan mutane sun zazzauna a cikin qawatattun runfuna da aka shirya musu musamman, sai gwamnan Arewa Sir Gawain Bell ya nufi Qofar Mata cikin mota, inda ya taradda Sarkin Kano tare da 'yan Majalisarsa sun zo taryensa a kan dawakai. Bayan ya gaisa da Sarki, sai shi ma ya haye doki har zuwa Qofar Kudu na gidan Sarki, inda aka shirya wannan shagali, 'yan Dokan badujala su ne suka share musu hanya, suna tafe suna ta kaxe-kaxe da bushe-bushe. Gwamna na biye tare da Muqaddashin Razdan na Kano, Mr. Mclinctock, Sarki kuma na biye da 'yan Majalisarsa da dogarai da 'yan sulke da 'yan kwalkwali har Qofar Kudu. Abin dai sai wanda ya gani.

Sarkin Musulmi tare da Sarkin Gwandu sune suka kai Sarkin Kano rumfar da Gwamna zai rataya masa lambar K.B.E. Daga nan Razdan ya karanta saqon Sarauniya na bada lambar, sa'an nan Gwamna ya miqa masa lambar. Sai aka varke da sowa don murna.

Kafin Sarkin Kano ya yi jawabinsa sai da ya yi godiya ga Ubangiji. Sa'an nan ya ce yana mai matuqar godiya ga Mai martaba Sarauniya. Saboda darajar da ta ba shi da kuma shaidar amincewa da ta bayyana masa a gaban jama'a. Ya ce daraja ce da ta shafi kowa ba cikin Kano kaxai ba, ta shafi kowa a cikin Jihar Arewa duka ya ce:

> *Na tabbata wannan shi ne lokaci na biyu da aka ba da irin wannan lamba a jihannan. Mu duka a qasar nan munyi fahari a lokacin da Mai martaba Sarkin Ingila George na 6 ya ga dai-dai ne ya baiwa Mai girma, Sir Abubakar irin wannan lamba. To, ni ma ina fahari da cewa ni ne mutumin Jihar nan na biyu da na sami irin wannan daraja. Na yi alqawari zan yi matuqar qoqarin da zan iya in nuna na dace da wannan amana da aka ba ni.*

Da ya juyo wajen samun mulkin kai sai ya ce:

Yau saura wata 18 mu ke zaton samun cikakken mulkin kai na Nijeriya. Mun lura da irin wahalcewahalcen da ke gabanmu, amma duk lokacin da na hangi waxannan wahalce-wahalce, sai na kan ji daxi in na tuna qasar nan za ta zama xaya daga cikin qasashen da su ke haxa kai da Ingila. Da taimakonsu da kuma jagoransu, in Allah Ya yarda qasarmu za ta yi ta ci gaba da arziqi.

Sarakunan da suka halarci bikin sune: Sarkin Katsina, Sarkin Zazzau, Lamixon Adamawa, Sarkin Gwambe, Sarkin Hadeja, Sarkin Katagum, Sarkin Gumel sai Sarkin Ilori. Sa'an nan ga Sarkin Bauci, Etsu Nupe, Tor Tiv, Sarkin Jama'are, Aku Uka na Wukari, Atta na Igala, Sarkin Kazaure, Sarkin Daura, Wazirin Sakkwato, Wazirin Barno da Mr. B. Greatbatch, babban Sakataren Ofishin Firimiya wanda shi ne babban Razdan na Kano a da.[1]

Bayan ya gama jawabinsa sai taro ya watse. Da daddare jam'iyyar NPC ta shirya wata qasaitacciyar rawa a Randabu Hotel saboda murnar bayar da lamban nan. Alhaji Maiwada, M.H.A ya shugabanci wannan liyafa.[2] Wannan qasaitaccen Sarki y ataimaka waje ciyar da Arewa gaba, musamman a harkokin mulki. A shekarar 1961 lokacin da Sir Gawain Bell ya tafi lifi na watanni uku. Sir Muhammad Sunusi ne ya riqe muqamin Muqaddashin Gwamnan Arewa.

Zamanin Sir Bryan Sharwood Smith, ya yi naxe-naxen Sarakuna da yawa ya kuma qware sosai wajen halartar shagulgulan naxin Sarakuna a Arewa. Babu Gwamnan da ya kai shi naxin sarauta da bada lambobin girma a jihar Arewa. Shekarar 1954 na da muhimmanci sosai a tarihin Arewa. Saboda an yi naxe-naxen Sarakuna da yawa. A wannan shekara ce Arewa ta samu Firimiya a farko. A lardin Sakkwato kuma Gwamna ya yi bikin naxin Sarakuna biyu a kusan lokaci guda. To, Mai Wandon Qarfe abin nema ya samu!

Naxin Sarkin Argungu Muhammadu

Sir Bryan mashahurin Gwamna ne wanda ba shi da na biyu wajen naxa Sarakuna a wannan Jiha. Bayan 'yan watanni da naxin Sarki Kano sai wasu bukukuwan naxe-naxen Sarkin Argungu da Sarkin Gwandu suka taso, saboda haka sai a ce abin nema ya samu Mai Wandon Qarfe ga ranarka. Aran Jumma'a kuma 11 ga Yuni, 1954 Mai girma Leftana Gwamna ya naxa Sarkin Argungu a gaban taron mutane da yawa. Duk uwayen qasa da Hakimai na qasar Arugungu sun taru a wannan rana. A jawabin da Sir Bryan ya yi wa Sarkin Argungu ya ce:

---

[1] GTK, Ta 866, Jumma'a 12/9/1958

[2] *Ibid*., 19/9/1958 shafi na 7

Ina gai da Sarkin Argungu, 'yan Majalisarsa, Sarakuna da mutane. Na ji daxi qwarai da na zo nan Argungu yau, don in naxa Sarki. Don shi sananne yake gare ni a lokacin da na yi aikin Di'o mai kula da qasar Argungu. Sarkin Argungu Muhammadu, kai xan Sarki na 28 ne, Sarki Muhammadu, kai ne kuma Sarki na 31 daga Sarki Kanta, shahararren mayaqin nan da ya yi mulkin da ya zama abin tunawa. Ka yi wa En'e ta Argungu aiki matsananci, sa'an nan kuma kana da ilimi da goguwa da mutane, wanda shi ne a ke nema ga shugabanci – ko da su magatakardan qauyuka ne, uwayen qauyuka ne, uwayen qasa ko 'yan Majalisa. Qwarewan nan da ka yi zai yi maka amfani, da aka zave ka shugaban mutanenka.

Naka qaramin aiki ne. Akwai waxansu a bisa ladabinsu ga wanda ya yi Sarki kafin ka, za su samu da wuya su goyi bayanka bisa zuciya xaya. Na roqe ka ka jure a inda jurewa ya kamata, sa'an nan ka haxa kan mutanenka gaba xaya bisa zama lafiya. Lallai ne ka zama a shirye ka ke ka saurari kuma ka zama tsare daga shawarwari 'Yan Majalisarka, sa'an nan kada ka yi saurin shawartar Razdan ko Di'o. Ka tabbata duk abin da yake salama ne ga mutanenka za ka sami taimako daga ni kaina da na mutanena.

Sarki Muhammadu, yanzu zan danqa maka kayan sarautarka: Ga takobin Kanta. Ga wannan takobi da Gwamna Lugard ya ba Sarkin Argungu yau shekara arba'in da suka wuce, da kuma kakaki biyu irin wanda Gwamna Lugard ya bayar. Yanzu kuma ga sandar sarauta. Daga qarshe kuma ga takardar naxa ka. Ka karanta ta a hankali a cikin lokacinka, sa'an nan ka lura sosai, abubuwan da ke ciki cewa, za su taimake ka.

Sarkin Argungu Muhammadu, ni da mutanenka mun danqa amanarmu gare ka. Kada ka yar da wannan amana. Ina yi maka fatar alheri a wannan sabon matsayi da ka samu. Allah Ya ja zamaninka ya taimake ka ka yi mulki sosai bisa kan mutanenka, ka taimake su su yaqi ci uku su ji daxin zama.

Bayan Leftana Gwamna ya gama jawabi, sai aka yi ta kawo musu jafi bisa dawaki. Aka ci gaba da sauran shagulgula.[1]

Naxin Sarkin Gwandu Haruna

Ran 11 ga watan Yuni ne Leftana Gwamna ya naxa Sarkin Argungu, kashegari kuma ya wuce Birnin Kabi don naxa Sarkin Gwandu. Mutane dubbai suka taru a Birnin Kabi, saboda shagalin naxa sabon Sarki. Qarfe goma na yi sai

[1] GTK, 22/12/1954 shafi na 6

ga Mai girma Leftana gwamnan Jihar Arewa Sir Bryan Sharwood-Smith ya iso. A nan mutane suka varke da sowa, suna gaishe shi. Kafin Leftana Gwamna ya iso, Sarki na zaune a wani wuri da aka kewaye, yana fuskantar inda Leftana Gwamna zai zauna. Mai girma na zaunawa sai 'yam badujala suka shiga aikinsu na kixe-kixe da bushe-bushe. Sa'an nan Sarki da 'yan Majalisarsa suka nufo wurin zaman Leftana Gwamna.

Leftana Gwamna ya miqe, sa'an nan liman ya zo ya rantsar da Sarki a gabansa. Mai girma ya yi wa Sarki jawabi, daga qarshe ya miqa masa sandar girma ta sarauta, takardar naxawa, da Alqur'anin Abdullahi da kwari da baka na Abdullahi. A nan Sarki ya yi xan jawabi na godiya.

Duka duka dai kamar dawakai xari biyar suka zo. Bayan wannan sai Mai girma ya tafi, Sarki kuma ya hau doki ya nufi fadarsa, 'yan Majalisarsa na biye da shi da uwayen qasa. Cikin waxanda suka halarci bikin naxin sarautar har da Sardaunan Sakkwato, Sarkin Yawuri da Razdan na Sakkwato, Mr. K.P. Maddocks.

A cikin jawabin da Leftana Gwamna ya yi wa Sarkin Gwandu har ya ce,

Sarkin Gwandu, kai da 'Yan Majalisarka, Sarakunanka da mutanenka na gaishe ku. Na ji daxi qwarai da na dawo Birnin Kabi, wadda na sani sosai, a kuma kan wannan shagali a gaban mutanen da suka taru don naxa Sarkin Gwandu Haruna.

Kai, Sarkin Gwandu Haruna, xan Sarki Basheru, kai ne Sarki na 18 a zuriyar Malam Abdullahi, xan'uwan wayayyen nan mai riqon addini, Shehu Xan Fodiyo (Allah Ya ji qansa, amin). Yanzu an zave ka bisa al'ada ka zama magaji ga kakanninka, ka zama shugaban mutanenka.

Zan tunar da kai Sarkin Gwandu Haruna, akwai aiki mai kyau da waxanda suka gaji wannan sarautar suka yi, tun naxa kawunka Haliru. Ka gaji kawunka, wanda ya shahara bisa mulki bisa gaskiya, wanda shahararsa ta mulki bisa gaskiya ta watsu ko'ina, ba sai a Jihar Arewa kaxai ba. Sir Yahaya ya samo wa Gwandu abin da mu ke qoqarin samo wa Jihar Arewa. Aikinka ne Sarkin Gwandu Haruna, ka ga an ci gaba da tafiyar da aikin.

Tabbatar gwamnati mai kyau shi ne gaskiya, wannan kaxai ma zai sa mutanenka farin ciki. Aikinka ne ka gani duk waxanda aka sakam ma ragamar aiki a qarqashinka suna aikinsu sosai, ba nuna tsoro ko son zuciya, sa'an nan suna tafiyar da aikinsu sosai ba zalunci. A wajenka kuma ko yaushe ka zama a shirye ka ke ka saurari shawarwari 'Yan Majalisarka, kada ka yi saurin

shawartar Razdan da Di'o. Na tabbata, Sarkin Gwandu, samun nasarar qasar Gwandu yana cikin hannu mai kyau.[1]

Bayan ya miqa masa kayan sarauta, sai ya taya shi murna, ya yi masa fatan alheri a cikin mulkinsa. Ya yi fatan mutanensa su ji daxi cikin wadata.

Jawabin Razdan Na Sakkwato

Kafin Razdan na Sakkwato Mr. K. P. Maddocks ya tabbatar wa jama'a, cewa Malam Haruna Sarkin Gobir na Kalgo, shi ne aka zava ya zama Sarkin Gwandu, sai da Razdan ya yi jawabi. A ciki ya bayyana sunayen manyan mutanen nan masu zaven Sarki na gargajiya, kuma ya shaida wa jama'a irin abubuwan da mutanen nan suka duba a cikin zavensu. Razdan ya ce,

Kun sani lokacin kakanninku, akwai majalisa, wadda bisa kan al'adar qasa ta kan zavi Sarki. A yanzu masu majalisan nan, su ne galadima, madawaki, magajin rafi, Alqalin alqalai da Sarkin Kabin Jega. To, waxannan masu zave sun taru sun yi shawara. A cikin shawara kuwa sun yi tunani ga abubuwa uku manya da a ke dubawa wajen zaven Sarki. Wato halin kirki da adalci. Girmama shari'a da dokar qasa. Sa'an nan da gwaninta ga sha'anin mulki. Da suka gama shawara suka shaida mini, cewa su duka sun yarda babu mutumin da ya cancanci ya hau gadon sarautar Gwandu sai Malam Haruna, Sarkin Gobir. Nan da nan na sanad da Leftana Gwamna, shi kuma ya ba ni amsa, cewa ya yarda da wannan zave.

Sarki Ya Rantse

Sabo da haka, Malam Haruna, tun ba ka shiga sarauta ba, ya kamata ka yi rantsuwar biyayya ga sarauniya da wakilanta, in ji Razdan na Sakkwato. Bayan da Sarkin Gwandu Haruna ya rantse, Razdan ya miqa masa sandan sarauta na Sarki mai daraja ta xaya, sa'an nan ya ci gaba da jawabinsa, ya ce;

Sarkin Gwandu, yanzu ka yi rantsuwar biyayya ga sarauniya da Leftana Gwamna da Gwamna, wakilanta. Sabo da haka da iznin Gwamna, na sanasshe ka, na kuma sanad da jama'a duka, yau kai ne Sarkin Gwandu, babu wani sai kai. Zuwa gaba kuwa Leftana Gwamna zai zo nan da kansa shi naxa ka a gaban jama'a duka.

Yau ka gaji Sarki, wanda duka mutanen Nijeriya suka yabe shi, saboda halin kirki da adalci da himma da riqon jama'a, ban da son

[1] GTK, 22/12/1954 shafi na 6

kai, ban da son zuciya, ban da tsoro, Sarki kuwa wanda ba ya son komai sai taimakon jama'a. An sani, babu shakka, aikin Sarki da harakokin sarauta suna da wuya, amma in ka nema kullum ka taka hanya, wadda shi ya bi, ka yi ainihin abin da ya yi dai-dai, abin kuwa da zai taimaki jama'arka, Allah zai qara maka qarfi, zai taimake ka a cikin qasaitaccen aikin da ka fara yanzu.

Allah Ya sa ka a cikin hanyar gaskiya. Allah Ya ba mu lafiya da tsawon rai shi kawo wadata ga wannan qasa da jama'arta, amin."

Bayan Sarkin Gwandu Haruna ya fara gayad da jama'ar da suka taru, a farkon jawabinsa ya ce:

Na bayyanad da biyayyata ga sarauniyar Ingila Elizabeth ta Biyu, da magadanta da gwamnan Ikko da Leftana gwamnan Kaduna. Ina godiya ga sabon Razdan na lardin Sakkwato da babban Di'o namu da sauran Turawa da suka taru a nan yau. Majalisarmu da Allah Ya qaddara su zave ni, na yi musu godiya.

Sauran jama'a, uwayen qasa da baqinmu, ina qara yi muku gaisuwar marigayi Sarkin Gwandu, wanda ba za mu manta da irin taimakonsa da adalcinsa ga jama'a ba. Yanzu ina qara tabbata muku, kamar yadda kuka sani, cewa ba ni da wani maqiyi a raina bisa yardar Allah.

Abin dake aikin shugabanci duka a taqaice mun san shi. Wato, faxin gaskiya, yin adalci, tsaron irli da mutunci, rashin zalunci da ko wane taimako na jama'ar da ke cikin hannun magabaci in da bin shari'a, umurni ko dokoki.

Ku kuma ne bayanmu wato talakawa, kuna da naku aiki da ya kamata ku fake don mu ji daxin juna, mu zama masoya. Shi ne taimakonmuda tsare hakkin shari'a, biyayya ga abin da an horar da yarda da sabbin dabaru da a ke kawowa don kiyaye lafiyarku da qara arziqinku da waye kawunanku.

Idan kuka dube mu kamar maqiyayanku ko malamanku, bisa soyayya da aminci, mu kuwa muka xauke ku abin kulawarmu, babu shakka da yardar Allah, komai zai tafi sosai yadda mu ke fata.

To, ina kuma son in tuna muku, cewa yanzu ana cikin shirye-shiryen hana zalunci, jahilci da lalaci, da waxansu al'adu masu wahalad da mutane. Don haka na roqa, kada ku dami kanku da tattalin goron sarauta. Ni ban ba da komai ba, don wannan matsayi. Don haka ba dalilin da zan zura idanu ga wani ya ba ni. Na rigayana samu, na ko gode wa Allah.

Mu tsaya bisa albashinmu, mu dai-daita shi da harakokimmu, yadda za mu ji daxin aikinmu ba fargaba, ba kasala. Allah Ya taimake mu cikin harakokimmu duka, ya tsare mu, ya sanya albarka ga aikinmu, ya ba mu lafiya da wadata, ya kyautata makomarmu, amin.[1]

A yanzu sai mu dawo kan bayanin gwamnatin Sir Bryan. Mai Wandon Qarfe ya yi bayani dalla-dalla akan abubuwan da gwamnatinsa ta yi, amma kaxan aka kawo, don a nuna misalai. A matsayinsa na Leftana Gwamna ya karaxe kusan duk lungunan wannan Jiha wajen shimfixa ayyukan ci gaban jama'a da naxe-naxen sarauta. Saboda haka babu wanda ya yi mamakin ganin likkafarsa ta qara ci gaba. Wannan mashahurin Bature ya sami qarin girma inda ya zama gwamnan Arewa na farko a Tarayyar Nijeriya.

Sir Bryan ya Zama Gwamna

A sakamakon tarurrukan da aka yi, sai ran 1 ga Oktoban shekarar 1954 aka cimma kafa Tarayyar Nijeriya. A wannan rana ce jihohin nan guda uku: Jihar Arewa, da Jihar Yamma da Jihar Gabas, aka ba su cin gashin kansu. Kowanensu ya samu Gwamna da zai mulkin Jiharsa. A wannan sabon tsarin mulki, an kafa Tarayyar Nijeriya wato Federeshan. A wannan lokaci, sai Leftanan Gwamna Sir Bryan Sharwood Smith ya zama gwamnan Arewa na farko, a cikin wannan tsari.

Kaduna, hedkwatar Jihar Arewa, ta cika da manyan baqi a wannan mako, domin naxa Sir Bryan Sharwood-Smith gwamnan Jihar nan. Ran 16 ga wata da safe, Sir Bryan ya iso Kaduna a jirgin sama, daga Ikko, tare da 'yarsa, Miss Angela Sharwood-Smith. Kafin qarfe goma, filin qofar *Lugard Hall* ya fara maqarewa da jama'a. Zuwar rabin sa'a, wuri a haxu. A kan benen qofa, Ministoci ne, su Firimiya, Sarkin Kano, Sarkin Zazzau, Aku Uka, da sauransu duka, suna jiran isowar Sir Bryan. Mutanen ofishin ba da labari sun shirya abubuwan xaukar sinima, suna ta xauka. Masu aikin rediyo sun shirya abubuwan qara girman magana. A cikin filin, an jera kujeru, Turawa da Baqar Fata, da Sarakunan da ke Kwas, kowa ya kama tasa. Kamfanin soja, 'yam Bataliya ta Huxu, sun jeru da makaxansu a baya. Zuwa can, Gwamna ya danno. Motar soja, *jeep*, tana gaba, ta Gwamna tana biye, soja 'yam babur sun yi mata banga-banga, sa'an nan motar babban Kwamandan sojan Arewa na biye.

Sir Bryan ya ci ado ya sa baqaqen kaya, na sarauta. Sun sha dajiya da dusar zinariya. Rigar da ya sa, irin mai bazan nan ce, ga hula da farin ga shi da ja, ga takobi, ga waxansu qululai tankas a kafaxunsa. Kai, kayan nan, haqiqa misalinsu sai wanda ya gani kurum.

---

[1] GTK, 27/1/1954 shafi na 4

Ya sauka ya tsaya, kamfanin soja suka sauke bindigogi, badujala da begila suka yi kixa da busa, irin wanda a ke kira *General Salute*, kowa na tsaye, Gwamna da waxanda ke da iko suka sara. Daga nan Keftin da ke duba fareti ya yi wo maci zuwa ga Gwamna, suka yi wata magana, sa'an nan Gwamna ya bi shi yakewaya sojan. Da ya dawo ya sake tsayawa, aka yi taken Sarauniyar Ingila, *Royal Salute*. Kowa na tsaye.

Gwamna ya haye benen qofar *Lugard Hall*, inda Ministoci da 'yan Majalisar Ministocin Jiha su ke jiransa. Mr. H.R.E. Browne, wanda ya zama muqaddashinsa lokacin da yake lifi, shi ne ya karanta takardar Sarauniya, ta iznin naxa shi Gwamna. Sai kuma Mr. Justice Stuart ya rantsar da shi, sa'an nan Gwamna ya sa hannu cikin littafin rantsuwar.

Daga nan Firimiya, Sardauna Ahmadu, ya yi jawabin maraba ga gwamnan farko na Jihar Arewa, tun daga Gwamna Lugga. Shi kuma Gwamna, kamar yadda Sardauna ya fara jawabi da turanci, ya qare da Hausa, Haka nan ya yi.

Sai Gwamna ya sauko, shi da 'yarsa, Miss Sharwood-Smith, ya dakata ya karvi gaisuwar soja, *Royal Salute*, sa'an nan ya shiga mota. Kamar yadda ya iso, haka aka yi. Motar soja, *jeep*, tana gaba, 'yam babur sun yi masa banga-banga, kwamandan soja na tasa motar a baya. Gwamna ya wuce filin sukuwa, inda soja su ke ta harba igogi, don murnar wannan sarauta. Sau 17 aka buga igogi. Gwamna ya duba su, sa'an nan ya wuce masauki. Kamfanin soja suka yi maci, badujala na tashi, sauran jama'a suka kama hanyarsu zuwa gida. Da Yamma aka sake gamuwa gidan Gwamna, Turawa da Baqar Fata, aka yi shaye-shaye da ciye-ciye. Dubban mutane sun halarci wurin naxa Gwamna, ban da wani soja da ya faxi, lokacin da su ke tsaye, babu abin da ya faru a wurin nan.[1]

A ranar Jumma'a, 17 ga Disamban shekarar 1954, ran nan aka yi shagalin naxa Sir Bryan Sharwood-Smith, ya zama gwamnan Jihar Arewa na farko a cikin Gyararren Tsarin Mulkin nan. Rabon Arewa da gwamnan kanta, tun Gwamna Lugga. Sir Bryan ya yi gajeren jawabi ran nan. Ya ce:

> *Na gode maka, Firimiya, domin kyakkyawar marabar da ka yi mini, wadda ta shiga zuciyata ainun. Ni da kai mun yi aiki tare, yau shekara da shekaru ke nan. Lallai kam ina ganin na yi sa'a, fiye da komai, da yake ga ni yanzu tsaye tsakanin tsofaffin abokai da yawa, na gaskiya, don kuwa bai kamata mu ruxi kammu ba, kwanakin da ke gabammu masu wuya ne, waxanda ke buqatar kawuna masu tunani a natse, da zuciyoyi masu qarfi.*
>
> *Mutane miliyan goma sha-takwas fa sun zura ido, a gare su ne kuwa za mu bayyana komai, sai fa dukammu, a kowane lokaci, tare da*

[1] GTK ta 641, 22/12/1954

kowane irin qanqan da kai, mu riqa tunawa da wannan. Akwai muhimman ayyuka da yawa da ke jiranmu, manya daga cikinsu kuwa, sune shafewa daga zukatan jama'a dukan tsoron zalunci da tsanani, tare da qara watsawar ilimin nan da fahintan nan, waxanda za su yi kowa da kowa qaimi, don ya rungumi haqqin da ke kansa na zama cikin jama'a, ba da wata kuskunda ba, kamar misalin yadda zai karvi abin da ya dace, mai amfani, don zama cikin jama'a, don kuwa in ba da waxannan abubuwa ba, ba za a sami arziqi mai danqo ba.

Irin babbar soyayar da ni da waxanda ke kewaye da ni mu ke da ita game da mutanen Arewa, Sarakunansu da shugabaninsu, na sani ita za ta qarfafa ni a kowane lokaci, a cikin dukan abin da ke niyyata, domin kyautata buqatummu, da buqatun haxaxxiyan Nijeriya, wadda mu ke ciki[1].

Firimiyan Jihar Arewa Sardauna Ahmadu, ya yi wa Sir Bryan Sharwood-Smith maraba, kafin a naxa shi gwamnan Jihar nan. Sardauna ya yi jawabi da Turanci, sa'an nan ya qare da Hausa. Ya ce:

Mai girma, Gwamna, da jama'ar da suka halarci wannan taro. Babbar girmamawa ce a gare ni da aka zave ni in isar da marabar jama'ar Arewa duka ga gwamnanmu na farko a nan Jihar Arewa, bayan Gwamna Lugga. Kuma babban abin farin ciki ne a gare ni, da shi ke mai daraja Sarauniyar Ingila ta ga ya cancanta ta naxa Sir Bryan Sharwood-Smith ya zama gwamnanmu na farko a cikin Sabon Tsarin Shirin Mulkimmu.

Na san shi tun da daxewa, kuma mun yi aiki tare da shi tun kafin ni da shi mu hau wannan matsayi da Allah Ya kawo mu.

Fiye da shekara 30 da ya yi yana bautawa qasar nan tamu ta Arewa, Sir Bryan ya nuna shi masoyin mutumen Arewa ne, kuma ya san al'adunmu, yana kuma girmamasu.

A zamaninsa da ya yi yana Leftana Gwamna ya gamu da rikitattun matsaloli, amma bisa ga shugabancinsa, an yi abubuwa da yawa da canje-canje masu amfani a cikin salama.

Na tabbata zai tuna, cewa wata rana na tava ce masa jama'ar Arewa suna yabawa da abubuwan da ya yi na ci da qasar nan tamu gaba. Wannan yabawa tasu kuwa, sun nuna ta ga takardun da su ke yi ga jaridu da kuma taxe-taxen da su ke yi a cikin hirarsu. Ina kuma

[1] GTK ta 641, 22/12/1954shafi na 6

son in tabbatar wa Sir Bryan, cewa babu abin da ya sake game da wannan yabawar.

Akwai rikitaccen lokaci a gabammu a cikin sha'animmu na nan Arewa, kai har ma na Nijeriya baki xaya, amma na amince qarfin halin Sir Bryan da tsinkayarsa sun dace da wannan lokaci, kuma buqatan nan ta samarimmu ta son ci gaba da sauri, zai wadace su da hikimarsa da gogayyarsa.

A yanzu ina son in tabbatar masa da nufina da kuma nufin Ministocina duka, cewa za mu yi matuqar qoqarinmu ba tare da son kai ba, mu taimake shi ga babban gurinsa, shi ne ciyar da qasar nan tamu gaba."[1]

Shi wannan mashahurin Bature, gwarzo ne kuma gwanin iya mulki ne, wanda ya daxe a Arewa yana hulxa xanya da mutanenta a kowane lungu. A tu'amulinsa da jama'ar Arewa ya fahimci nagartarsu da qwazonsu da kuma amincinsu. Sannan kuma ya fahimci matsololin da suke fuskanta, waxanda a lokuta masu yawa ya kan taimaka wajen maganinsu. Don haka shi ya fi dacewa da ya zama gwamnansu.

Haka kuma Sir Sharwood Smith ya sami amincewar Sarakunan Arewa, waxanda yake tare da su, yana kuma ji da aiki da shawarwarinsu. Ya kuma yi ayyuka masu yawa da amfani da za su taimakawa wannan jiha wajen fuskantar qabulen da zamanin siyasa ya kawo. Kusan kowa ya san wannan gwamnan mutumne amintacce, wanda ke sauraron kukan jama'a a ko da yaushe. Yana kuma yin iyakar qoqarinsa wajen share masu hawaye.

A lokacin mulkinsa ya kawo abubuwa biyu sabbi; shi ne ya kawo Tsarin Mulkin Ministoci a Arewa, *the Ministerial System of Government in the North*." Shi ne kuma ya qirqiro da muqamin Mataimakan Di'o na farko a Arewa, *First Northern Assistant District Officers.*[2]

A lokacinsa ne Sarauniya ta ziyarci Arewa a shekarar 1956. Shi ne ma mai masaukinta da ayarinta. Shi kansa sai da ya tsinke da Arewa wajen nuna karimci da biyayya ga Sarauniya. Sir Bryan Smith, ya yi Gwamna a qasar nan a lokaci mai wuya, ya kuma taka rawar gani wajen yin ayyukan da suka kawo ci gaba. Wannan ya sa, ya samu yabo daga kusan kowa da kowa. Hasalima hatta gwamnatin Nijeriya ta Arewa ta lokacin, a cikin wani xan littafi na ban kwana da Mai Wandon Qarfe, mai suna *The End of an Era* yabonsa ta yi.

Mai Wandon Rarfe, zai yi ritaya, zai kuma bar Nijeriya ta jirgiin sama daga Kano ran Alhamis, 19 ga Satumban shekarar 1957 zuwa Ingila, inda zai yi xan

---

[1] GTK 22/12/1954 shafi na 6.

[2] Abubakar Imam, *Auren Zobe*; *Abutar Nijeriya Da Ingila*, Shafi 9.

lifi, kafin ya yi ritaya. Mai girma da Uwargidansa, Lady Sharwood-Smith, suna da niyyar su zauna dindindin a Ingila.[1]

Sai Wata Rana Sir Bryan

A ran Laraba 18 ga watan Satumban shekarar 1957, Majalisar Sarakuna ta yi zama na kwana guda saboda bankwana da shahararren gwamnan Arewa, Sir Bryan Sharwoo-Smith, wanda zai koma Ingila, ba zai dawo ba don zai yi ritaya. A wannan zama ne Sarakuna da yawa suka yabi wannan gwamnan mai ritaya tare da Uwargidansa, Lady Sharwood-Smith, saboda daxewa da suka yi suna yiwa jama'ar Arewa ayyukan ci gaba. An shaqu da su sosai, su ma sun shaqu da Arewa da jama'arta. Sun kuma cancanci yabo saboda sun sadaukar da kansu wajen aikin jama'ar wannan Jiha a shekaru da dama.

A wannan zama ne kuma Sarkin Musulmi Sir Abubakar, ya gabatar da shirin doka kan batutuwa tara waxanda za a sawa hannu ba tare da mahawara ba, a inda Sarkin Kano, Alhaji Muhammadu Sunusi, ya goyi bayansa. Majalisar kuma ta rattaba hannu a kan su. Waxannan batutuwa 'yan Majalisar Wakilai sun rugaya sun sa masu hannu. Kashe gari, sai Sarakuna da Wakilai da sauran jama'a suka hallara a tashar jirgi ta Kaduna Jamsin wajen bankwana da Mai Wandon Qarfe, inda za su ce masa adabo sai wata rana!

An yi qasaitaccen bikin bankwana da wannan Gwamna mai ritaya a Kaduna a dai-dai inda taragan jirgin da zai kai gwamnan zuwa Kano. A farkon shirin tashin sa zuwa Ingila, sai da aka yi bikin yi masa adabo, Sai wata rana a Kaduna Jamsin. Manyan baqi sun halarci wannan biki wanda ya kawo taron ximbin jama'a masu son ganin sa a wannan waje, kowa na son ganin qasaitaccen mutum da zai koma gida, kuma kowa hankalinsa a tashe saboda jama'ar Arewa da yawa sun shaqu da shi.

Manyan mutane sun fara zuwa wajen wannan biki da misalin qarfe takwas da minti talatin da biyar na safe (8:35am). Firimiya, Sir Ahmadu Bello, da, Sir Abubakar na Uku, da Cifjojin Jihar Arewa har sun iso sun kama kujerunsu a wajen wannan biki na bankwana da Sir Bryan Sharwood-Smith. Mai girma Gwamna mai ritaya ya iso Tashar Jirgi wajen wannan taro tare da Kantoman Kaduna Mr.R.N Barlow-Poole. Amma kafin ya kai dandamalin manyan baqi, sai da ya duba faretin bangirma wanda Sojan 1st Field Battery suka yi masa, tare da 'yan badujala suna kaxe-kaxe da bushe-bushe, qarqashin jagorancin Keftin J.D.West.

Daga nan sai Mai girma da Uwargidansa suka gaisa da manyan baqi. Lady Sharwood-Smith, Uwargidan Mai girma, sai ta karvi kyautar filawoyi daga Fatima Habib, 'yar Malam Abba Habib, Ministan Ciniki da Masana'antu na Jihar

[1] GTK, ta 808, 2/8/1957.

Arewa. Bayan haka, sai `yan Begilan Bataliya ta xaya, wato 1st Battalion suka yi kaxe-kaxe da bushe-bushe na bankwana da Hausa. A wannan lokaci kuma sai aka riqa saukar da tutar Mai girma a hankali.

Sir Bryan Sharwood-Smith ya fashe da kuka a lokacin da zai shiga jirgin qasa zuwa Kano, sai hawaye ke zubo masa shar-shar yana shArewa da hannunsa mai safa. Taragon jirgin da ke xauke da shi ya bar Kaduna Jamsin a kan hanyar sa zuwa Kano da misalin qarfe tara da qwata na safe, (9:15am) a ran Alhamis 19 ga watan Satumban shekarar 1957. A cikin manyan mutanen da suka raka Gwamna da Uwargidansa zuwa birnin Kano sun haxa da: Firayim-Minista, Alhaji Abubakar Tafawa Valewa, da Alhaji Isa Kaita, Ministan ilimi na Jihar Arewa da Sakataren Gwamna.[1]

Maraba da Sir Gawain Bell

Sabon gwamnan Jihar Arewa, Sir Gawain Westray Bell, ya zo ya kama aikinsa. Kaduna ta ga babban taro a ranar da aka yi shagalin rantsar da sabon Gwamna a *Lugard Hall*. Ran nan Firimiya ya yi masa maraba, shi kuma ya amsa da kalmomi masu daxi. A wannan rana da qarfe goma na safe, (10am) Sir Gawain ya isa *Lugard Hall* inda masu begila suka yi wata busa mai daxi. Muqaddashin Gwamna, Mr. K.P Maddocks, da Firimiya, da Cifjojin Arewa, wakilin muqaddashin mataimakin Gwamna, da wakilin shugaban Majalisa, da wakilai da Akawun Majalisa suka tarye shi, suka shiga majalisar.

Cif Jojin Jihar Arewa ya rantsar da Gwamna, sa'an nan su biyu suka sa hannun aikin a littafin rantsuwa. Daga nan sai Alhaji Sir Ahmadu ya yi jawabin maraba ga Gwamna, sabili da Jihar Arewa da jama'arta. Firimiya ya ce yau shekara uku ne nan shugabannin Jihar Arewa ke riqe da al'amuranta. Ya ce sun yi sa'a da suka samu Sir Bryan ne ke gwamnan Jihar, domin shi ya qare lokacinsa ne cikin aiki a Arewa. Ya san mutanen Arewa, kuma mutum ne mai wayo, mai kuwa ganin darajar xabi'oi na aladun Arewa. Don haka suna cike da godiya ga Sir Bryan.

Firimiya ya ce shekarun nan uku sun shuxe. Cikinsu ne aka fara aiki da sabbin shirye-shiryen sha'anin mulki, waxanda aka gina bisa harsashin irin tsarin mulkin 'yan qasa: Ya ce, ko da yake ba mu da kammu ne ya kamata mu ambata irin nasarar da muka yi ba, kowadda ba mu yi ba, duk da haka dai mun ci gaba ainun wajen kintsa kammu yadda za mu iya xaukar nauyin mulkin kammu a wannan zamani na yanzu.[2]

---

1 NC, ta 560, Asabar 21/9/1957

2 GTK, 6 ga Disamba, 1957

Firimiya ya ce suna da ximbin aikin da ke gabansu a qasar nan - qasa wadda in an tara faxinta da tsawonta yakai mil dubu xari biyu da tamanin (280,000), ga jama'a miliyan goma sha-takwas (18), masu harsuna da xabi'o'i iri daban-daban. Ya ce;

Mu na ganin darajar kowane abu namu na da, wanda yake kyakkyawa ne. Muna girmama na gabanmu qwarai, sa'an nan mutane ne mu masu son zama lafiya da gamuwar kai, amma ba gamuwa a komai da komai ba. Daga nan sai ya da juya kan abubuwan da su ke hange a gaba. Ya ce Gwamna ya zoqasar nan cikin wani muhimmin lokaci. Ya qara da cewa: "Muna shirin juya sabon shafi ne cikin tarihin qasar nan. Yana da wuya mutum ya kwatanta abin da zai auku gaba.

Ya ce amma mun sani muna iya dogara da cikakken hankalin jama'ar Arewa su tsaya tsayin daka bisa abubuwan da za su amfani Arewa. Yaci gaba da cewa muna sa rai Gwamna ya yi muna taimako, musamman dayake yana da ilimin tafiyar da mulki da ya samu a waxansu qasashe. Game da sha'anin ma'aikata, Firimiya ya ce:

Maganar danqa wa 'yan Arewa jagorancin Arewa tana shan suka daga 'yan siyasa, da jaridu da jam'iyyoyin ma'aikata a Nijeriya duka. Yanzu ma mun yarda cewa wannan tsari shi ne zai warkad da wahalar da a ke sha wajen samun ma'aikatan gwamnati.[1]

gwamnati a dage take kan cewa shirinta ta ba da qarfinta ga koyawa, 'yan Arewa maza da mata su koma ayyukan Jihar nan. Waxanda ba 'yan Arewa ba ana maraba da su, musamman in sun nuna soyayya ga buqatun 'yan qasa, da kuma gwanintar aiki. Ya ce;

Mun kam shayin samada qasa, amma dai muna tafe sosai lafiya. In wani abu ya auku, a kan tafiyar da shi ta hanya da ya kamata, ba a bayyana wa duniya ba, don kawai neman farin jini. Ina son gwamnatin nan ta lura da abubuwan nan da na ambata.[2]

Sabon Gwamna Sir Gawain Westray Bell, ya amsa jawabin nan. Ya yi murna da Allah Ya kawo shi Jihar Arewa, musamman da yake yafi shekara goma sha-biyar (15) yana qasar da ke maqwabtaka da Arewa, itace qasar Sudan. Ya ce yasha jin labarin Arewa, ya kuwa sha saduwa da mutanenta masu zuwa Sudan da

---

[1] GTK, 6 ga Disamba, 1957

[2] *Ibid*. shafi na 10

waxanda ke zaune can. Saboda haka tun da aka naxa shi gwamnan Arewa sai ya yi ta karanta duk abin da ya samu na labarinta. Ya ce irin bambancin da ke akwai a Arewa zai firgita baqo, kafin ya gane, saboda haka ne ya ce:

> *Amma zan ziyarci ko'ina, domin in gane wa idona yadda qasar take. Na zo qasar nan cikin muhimmin lokaci, Arewa na kan dandamalin mulkin kai.*
>
> *Irin canje-canje da mulkin kai zai kawo, lallai a sanya haquri da hangen nesa da dabara. Lallai a hangi gaba, abin da zai zo yau, da gobe, har ma da jibi, a yi lissafi da shi. Lallai mu shirya yanzu irin muqamin da 'ya'yanku za su shiga, magadanku. Zan daidaita ayyukana da majalisata, yadda irin mulkin kai ya zo, komai zai tafi sosai yadda kyakkyawar gwamnati da ta shari'a, wadda aka sha faman ginawa ba za su rushe ba.*
>
> *Ya yarda Jihar Arewa tana da waxansu kyawawan al'adu da halaye waxanda in an cuxanya su da abubuwan zamani kyawawa, za su inganta qarfafa al'amura, irin yadda za a bukace su a shekaru masu zuwa.*[1]

Gwamna ya ce harsashen kowa ce qasar da ke da nufin aikin kirki, tare da jin daxin jama'arta, yana xore bisa kyakkyawan aikin ma'aikatanta ne. Wannan magana musamman ta sa Arewa, inda aka yi ayyuka kyawawa da yawa, ana kuwa buqatar a ci gaba da su. Domin haka ne ya ce lallai a sami fahimtar juna tsakanin gwamnati da ma'aikatan Turawa da Baqar Fata. gwamnati da tana sa rai ma'aikanta su yi mata kyakkyawan aiki, su kuma suna sa rai gwamnati ta yi musu kyakkyawan riqo." In an sami haka nan da nan qasa za ta kai ga burinta.[2]

Da zuwan wannan sabon Gwamna sai Muqaddashin gwamnan Arewa ya samu qarin girma, Likkafar Mr. Maddocks ta yi gaba. Sakataren kula da Qasashen da ke Qarqashin Mulkin Ingila, Mr. Alan Lennod-Boyd ya ba da labari cewa Mai martaba Sarauniya ta yi farin cikin naxa Mr. K. P. Maddocks, Muqaddashin gwamnan Arewa ya zama gwamnan Fiji maimakon Sir Ronald Garvey, wanda wa'adin muqamin Gwamna da aka xeba masa zai qare cikin Oktoba. Ana tsammani a qarshen Oktoba Mr. Maddocks zai xauki sabon mulki.

A cikin shekarar 1929 Mr, Maddocks ya zo Nijeriya, ya yi aiki a lardin Kano da Binuwai da qasar Kuza. A shekarar 1940 zuwa 1944 ya yi aiki a Sakatariyar Nijeriya a Ikko. Ya yi aikin akawun Majalisar Dokoki da Majalisar Gudanarwa daga shekarar 1943 zuwa 1944.

---

[1] GTK, 6 ga Disamba, 1957 shafi na 10

[2] *Ibid.*

A shekarar 1951 ya dawo lardin Qasar Kuza inda ya zama sau uku yana aikin muqaddashin Razdan kafin a naxa shi Razdan a shekarar 1951, a wannan shekara, aka tura shi Kano. A shekarar 1952 ya sake komawa Ikko ya yi aikin Sakataren mulki har na wata goma sha-biyu kafin ya dawo Arewa ya yi aikin Razdan a Sakkwato. A Janairun shekarar 1955 aka naxa shi Sakataren Mulki na Jihar Arewa, sa'an nan a watan Satumba na shekarar 1957 ya zama Muqaddashin Gwamna lokacin da aka soke muqamin Sakataren mulki.

Kafin ya tashi daga Kaduna zuwa gida lifi sai da Firimiyan Arewa ya shirya wata qasaitacciyar liyafa dominsa. Mutum xari biyar suka halarci liyafar. Haka kuma wajen mutane xari suka rakashi filin jirgin saman Kaduna, ciki har da sabon gwamnan Arewa, da Firimiya da Ministocinsa, da babban cifjojin Arewa. A wajen liyafar yi masa bankwana, Firimiyan Jihar Arewa ya ce:

> *Yau wata takwas ke nan da suka wuce a taro irin wannan muka yi bankwana da Sir Bryan Sharwood Smith, ko kuma kamar yadda aka fi saninsa, Mai Wandon Qarfe. Bayan wannan muka yi maraba da sabon gwamnanmu, Sir Gawain Bell, wanda har yanzu ba mu raxa masa laqabi ba, amma na tabbata nan gaba za mu raxa masa. Mun taru a wannan fili na tarihi don mu yi bankwana da babban mutum da aka shaqu da shi a Arewa wanda zai bar mu. Ina nufin Mr. K. P. Maddocks, Muqaddashin gwamnanmu.*[1]
>
> *Bayan Firimiya ya faxi tarihin Mr. Maddocks da irin aikace-aikacen da ya yi, sai kuma ya juya kan uwargidansa, wadda tayi taimako qwarai wajen inganta kula da yara a Kaduna . Daga nan ya ce "Sai mu yi fatan jin daxi a sabon gidansu, kuma mu yi fatan ba za su manta da mu ba. Ba shakka mu kuma za mu riqa tunawa da su.*[2]

Cikin amsar da Mr. Maddocks ya bayar, ya ce shi da uwargidansa sun gode wa Firimiya da kalamominsa na bankwana masu daxi, ya ce ba shakka za su yi baqin cikin rabuwa da Nijeriya. Amma ya ce har abada ba za su bar begen Arewa ba. Ya ce sabon muqamin da zai samu zai xauke shi nesa daga Nijeriya. Ya ce "Abin baqin ciki ne hanyar da za mu bi, ba za ta biyo ta Nijeriya ba."[3]

---

1 GTK, 6 ga Mayu, 1958.

2 *Ibid*. shafi na 8

3 *Ibid.*

Gwamnatin Sir Gawain Bell

Sir Gawain Westray Bell, KCMG, CBE shi ya gaji Mai Wandon Qarfe a matsayin gwamnan Jihar Arewa daga shekarar 1957 zuwa 1962. A lokacinsa an sami ci gaba wajen harkar siyasa. Domin Arewa ta samu mulkin kanta a ran 15 ga Maris xin shekarar 1959. A lokacinsa ne kuma Tarayyar Nijeriya ta sami 'yanci kuma ta shiga qasashen da ke aminci da Ingila, a ran 1 ga Oktoban shekarar 1960. Ta kowace fuska, zamaninsa muhimmi ne a tarihin Arewa. A jawabinsa na Gwamna ga 'yan Majalisar Wakilai ga kaxan daga cikin abin da ya ce game da manufofin gwamnatinsa:

Wannan ne Jawabin farko da na sami falalar yi muku. Ina so in fara da cewa na xauki wannan abu bisa babbar daraja ce gare ni, wadda ba ta da abin kwatanci im ba darajan nan ta muqamin gwamnan Jihar nan ba kaxai.

Kafin in shiga zana muku irin abubuwan da Ministocina suka yi niyyar aikatawa cikin shekara mai zuwa, dole ne in ambaci ci gaban nan na Taron Shirin Mulki, da irin canje-canjen da ake tsammanin za su gudano daga gare shi.

Qungiyoyin Binciken nan guda uku da aka yarda a kafa a taron tarko na Shirin Mulkin nan da aka yi bara a London, duk sun fara aiki a Nijeriya cikin 'yan watannin baya, lokacin da aka ci gaba da Taron a qarshen shekaran nan. Shawarwari da za a yanke a lokacin, babu shakka za ta kawo babban tasiri ga rayuwar Nijeriya ta nan gaba. gwamnatina tana sane da alhakkin nan mai nauyi da take xauke da shi, ta kuwa quduri niyyar cewa Ala-Kulli Halin za ta tsaya ne bisa ga abin da yake alherin Jihar Arewa wanda kuma ba zai kawo lahani ga zaman Tarayyar Nijeriya baki xaya ba.

A cikin Jawabin Gwamna na bara, wanda Sir Bryan Sharwood Smith ya yi muku, ya bayyana cewa, ga tsammani, Arewa za ta sami cikakken mulkin Jiharta a cikin zamanin wannan Majalisa. gwamnatina tana ganin yanzu lokaci ya yi, don haka tana da niyyar kawo wani batu gaban Majalisan nan, bisa roqon Mai Alfarma Sarauniya ta yarda, cikin karimcin nan nata, ta tabbatar da mulkin kai ga jama'ar Jihar Arewa, waxanda ba su da na biyu wajen biyayya gare ta, a ran 15 ga watan Maris na shekarar 1959.

To, bari kuma mu juyo ga sha'anin da ke gaban gwamnati. Ministan Kuxi, a cikin jawabinsa na farko kan Istimat, zai kawo Dokar Kasafin Kuxin Shekara, wadda a bana, ta shirya Azuzuwan Kuxin Kashewar Yau da Kullum guda talatin da huxu, waxanda jimillarsu duka ta kai fiye da fam miliyan goma sha-uku. Ban da

wannan kuma, an tsara wani Istimat daban na Manyan Ayyuka, wanda a cikinsa za a kashe fiye da fam miliyan takwas. Jawabin Ministan Kuxi kan Istimat xin nan zai ba ku bayani sosai, kamar yadda aka saba, kan sha'anin kuxin Jihar nan da halin arziqinta.

Har yau kuma a bana gwamnatina tana fatar samun rancen kuxin Manyan Ayyuka don sha'anunuwan Raya Qasa, waxanda za su kai jimillar fam miliyan uku da rabi. Daga cikin jimillan nan, fam miliyan uku don shana'unuwan gwamnati ne baki xaya, wajen aiwatar da Tsarin nan na Raya Qasa. Fam rubu'in miliyan shi ne Rancen nan na Kyautata sha'anin musamman, wanda Majalisan nan ta yarda da shi a Taronta na Istimat na bara. Sauran fam rubu'in miliyan xin kuwa don a sake ba da rancensu ne ga En'e-En'e. Daga cikin jimillan nan, £1,500,000 za a nemo su ne daga hanyoyin waje, ragowar kuma Hukumar Cinikin Jihar nan ce za a roqa ta ba da su.[1]

A vangaren Ilimi Gwaman ya ce:

A 1958, ana fatar fara aiki a kan Makarantar 'yan Mata ta Lardin Bauci, da kuma sabbin gine-gine a Makarantar Horar da Malamai Mata ta Kano. Amma a nan wajibi ne a fayyace cewa im ba an iya samo qarin Turawan Makaranta mata ba, kuma muddin 'yan mata Musulmi da yanzu su ke ta fara qin yarda su zama malamai, ba su rage yin haka ba, tsare-tsaremmu na ilimin mata za su daxe ainun ba su kai ga biyan buqata ba.

Wajen ilimin Manya, za a maida qarfi wajen kula da qayyade buxe azuzuwan Yaqi da Jahilci barkatai, a riqa kashe kuxin da ake da su ta hanya mafi kyau.

Wajen Ayyukan Asibiti da na Lafiya, za a ci gaba da mai da qarfi ga kyautata hanyoyin horarwa. Makarantar Horar da Mataimakan Aikin Asibiti ta Kaduna, wadda aka buxe bara, almajiran cikinta za su cike ta duka sosai a watan Afrilu. An fara ginin Makarantar Horar da Masu Aikin Nas, ana kuwa fatar cewa wajen qarshen shekaran nan, har za ta shirya xaukar almajiranta na farko. Haka kuma za a qara girman makarantar Aikin Nas ta Kano. Makarantar Haxa Magani ta Zaria za a kai ta ga Matsayin samun Takardar Diploma ta Masu Aikin Kimiyya da Haxa Magunguna. Haka kuma za a qara ma'aikatan

---

[1] AH/GP/SA 19: Mai girma Sir Gawain Bell, Jawabinsa ga 'yan Majalisar Wakilai, na ran 19 ga Fabrairu, 1958, shafi na 1.

Makarantar Asibitin Kano, don a tanadi koyar da fani masu zurfi, tun da yake yanzu almajiran nan za su shiga shekararsu ta huxu ke nan.

An kuma himmatu wajen gyaran garuruwa. An kuma ba Ma'aikatar Safiyon Nijeriya ta Arewa umarni da ta ci ga ba da shirinta na taswirori, ana fatar cewa kafin qarshen shekaran nan za a buga sabbin taswirori na zamanin yanzu, na qasashen da ke tsakanin Katsina-Keffi-Yola-Gaidam, da kuma gavar Arewa. Duka taswirorin nan za a shirya su ne bisa hoton da aka xauka ta jirgin sama. Haka kuma wajen tsarin garuruwa, gwamnan ya ce:

Akwai manyan tsare-tsaren garuruwan Kano da Kaduna da sauran manyan garuruwa waxanda yanzu a ke cikin yi. Ana kuma fatar cewa shekara mai zuwa za ta zo da qarin Ma'aikatan Tsarin Garuruwa don su iya tasar ma matsalolin nan na Jihar nan da ke qara yawa, na sha'anin raya birane. Ana ganin zai zama wajibi ainun a yi wani tsari na can gaba don kewayen alqaryar Kano, saboda haka za a aika da Baturen Aikin Tsara Garuruwa can, ba da daxewa ba.

Tushen manufar sha'anin mulkin En'e shi ne a haxa duka dangogin jama'a, takan wakilansu a Majalisa, a matsayi daban-daban, inda za su iya sakewa su yi shawara kan buqatunsu da matsalolinsu, yadda ta haka za su tabbatar da cewa ana biyan buqatunsu na gaskiya kuma waxanda suke dai-dai. Za a ci gaba da ba da qaimi ga qara buxa Majalisun En'e, gwargwadon buqata, kuma bisa yadda ya dace da kiyayewar iko da kuma kyakkyawan mulki.[1]

Sir Gawain Bell ya qara da cewa:

Za a ci gaba da aiki kan qare-qaren ayyukan Famfo a Kaduna da Zaria da Jos. Ana fata famfon Maiduguri da Katsina za su fara aiki cikin shekarar nan. Aikin Rijiyoyi shi ma yaci gaba da kyau ainun har zai gama shirin nan nasa na shekara biyar a farkon shekarar 1959, wato saurin shekara guda ke nan. Za a ci gaba da aikin haqar rijiyoyin nan, tare da rarake tafkuna.

Maganata ta qarshe ita ce kan manufar nan ta ba da ayyuka ga 'yan Arewa. gwamnatin Jiha za ta ci gaba da matsa wannan manufa da duk iyakar qarfinta. Kimanin 'yan Arewa da ke aikin gwamnati har yanzu kaxan ne ainun, amma ba za a iya ba da aiki ba sai lokacin da aka sami samarin da ke da da kuma horo waxanda suka dace.

---

[1] AH/GP/SA 19: Mai girma Sir Gawain Bell, Jawabinsa ga 'yan Majalisar Wakilai, na ran 19 ga Fabrairu, 1958, shafi na 5

Samuwar waxannan da yawa ya dogara ne ga yawan fitowa daga makarantu da wuraren koyo, da kuma Kwas xin nan daban-daban na Horarwa Musamman, waxanda aka shirya. Za a yi duk iyakar abin da a ke iyawa don a gaggauta wannan. Shugaba, da Mashawarta, ina roqon Allah Ya sa aikinku a Majalisan nan ya zama, cikin shiriyar Ubangiji, mai amfani ne.[1]

Gwamna sai ya juya wajen Sarakuna. Ya yi jawabi ga Majalisar Sarakuna a ran 17 ga Maris na shekarar 1958. Mai girma Gwamna ya ce:

Sarakunan Jihar Arewa

Ina so in fara da cewa babbar daraja ce gare ni da na sami yi muku jawabi na farko a yau. A cikin Jawabin Gwamna na bara, wanda Sir Bryan Sharwood Smith ya yi muku, ya bayyana cewa, ga tsammani, Arewa za ta sami cikakken mulkin Jiharta a cikin zamanin wannan Majalisa. gwamnatina tana ganin yanzu lokaci ya yi, don haka tana da niyyar kawo wani batu gaban Majalisan nan, bisa roqon Mai Alfarma Sarauniya ta yarda, cikin karimcin nan nata, ta tabbatar da mulkin kai ga jama'ar Jihar Arewa, waxanda ba su da na biyu wajen biyayya gare ta, a ran 15 ga watan Maris na shekarar 1959.

To, bari kuma mu juyo ga sha'anin da ke gaban gwamnati. Ministan Kuxi, a cikin jawabinsa na farko kan Istimat, zai kawo Dokar Kasafin Kuxin Shekara, wadda a bana, ta shirya Azuzuwan Kuxin Kashewar Yau da Kullum guda talatin da huxu, waxanda jimillarsu duka ta kai fiye da fam miliyan goma sha-uku. Ban da wannan kuma, an tsara wani Istimat daban na Manyan Ayyuka, wanda a cikinsa za a kashe fiye da fam miliyan takwas.

Har yau kuma a bana gwamnatina tana fatar samun rancen kuxin Manyan Ayyuka don sha'anunuwan Raya Qasa, waxanda za su kai jimillar fam miliyan uku da rabi.

Aikin Gona har yanzu shi ne sana'ar da ta fi kowacce a Jihar nan, kuma shi ne babban tushen arziqinta. Shekara goma da suka shige kayan gonar da Jihar nan ke fitarwa qetare ba su kai ko rubu'in yawan kayan gonar fitarwa na Tarayyar Nijeriya ba. A shekarar 1958 qila kayan gonar fitarwa daga Jihar nan za su kai har rabin duka kayan gonar fitarwa na Nijeriya bai xaya. Za a matsa ci gaba da taimakon sana'ar nan ta noma. Aikin nan na yaxa irin gyaxa mai

---

[1] AH/GP/SA 19: Mai girma Sir Gawain Bell, Jawabinsa ga 'yan Majalisar Wakilai, na ran 19 ga Fabrairu, 1958, shafi na 5

lamba K.50 a Lardin Kano, za a qara buxa shi. Haka kuma irin audugan nan ta Allen "26C" wadda ta ci nasara ainun, da irin ta Binwai"wadda ba a yanka mata daraja ba," za a ci gaba da musanya su da mai lamba "26F" wadda aka qara kyautatawa. Za a qara ci gaba da qoqarin tallar takin zamani, kuma za a ci gaba da nuna amfanin yadda ake gyara shukar iri a ko ina.

Za a miqe aikin nan na kyautata wuraren kiwo zuwa wasu sabbin wurare a Lardunan Kano da Katsina da Sokoto, kuma matsalar nan da ke qara tsanani ta rojewar qasa, za a qara ba da kula gare ta.

Shirin nan na Aikin Dabbobi zai haxa da qara buxa aikin kashe qudan tsando. A shekarar 1956-57 fiye da shanu 560,000 aka yi wa allurar ciwon sammore, kuma a shekara mai zuwa nan tsammanin adadin zai doshi 700,000.

Jihar nan za ta gina Makarantar Dabbobi takanta a cikin shekaran nan, ana kuwa fatar qare aqalla xaya daga cikin gidajen mayankan nan na zamani.

Aikin nan na qara kyautata qiraga da fatu zai ci gaba da kiyaye darajar waxannan muhimman kayan fitarwa qetare.

Har yau kuma ana nan ana tsare-tsaren gina wurin aikin Jima na gwaji, don a sami dabarun da suka dace na kyautata, da buxa, sana'an nan ta jima.

Muhimman aikace-aikacen Yankin Aikin Daji za a ci gaba da mai da qarfinsu, a shekara mai zuwa, ga keve tabbatattun gandayen daji. Za a shirya sarrafar da gandayen dajin nan da sauransu a duk inda ake matse da buqatar kayan amfanin dajin nan. Za a buxe makarantar aikin daji a Naraguta, kusa da Jos, don horon Malaman Daji na En'e, cikin shekaran nan.

Wajen Sha'anin, samun 'yan qasa maza da mata waxanda ke da issashen ilimin bauta wa qasarsu a cikin shekarun nan mawuyata da ke gaba, zai ci gaba da qaruwa a hankali a hankali. A cikin shekaran nan, almajirai wajen 420 ne a Jihar nan za su xauki Babbar Jarabawar Makaranta: wannan qaruwa ce ta kimanin kashi 60 cikin 100 bisa adadin waxanda suka xauka a bara.

Wajen fuskar ilimin Sana'a, Makarantar Sana'a ta Ilori za ta xauki azuzuwanta na farko a watan Maris, haka kuma za a buxe sabbin Makarantun Sana'ar Hannu da yawa cikin shekaran nan. Ana fatar fara aiki a kan Makarantar 'yan Mata ta Lardin Bauci, da kuma sabbin gine-gine a makarantar Horar da Malamai Mata ta Kano.

Wajen Ayyukan Asibiti da na Lafiya, za a ci gaba da mai da qarfi ga kyautata hanyoyin horarwa. Makarantar Horar da Mataimakan

Aikin Asibiti ta Kaduna, wadda aka buxe bara, almajiran cikinta za su cike ta duka sosai a watan Afrilu. Am fara ginin Makarantar Horar da Masu Aikin Nas, ana kuwa fatan cewa wajen qarshen shekaran nan, har za ta shirya xaukar almajiranta na farko. Haka kuma za a qara girman Makarantar Aikin Nas ta Kano. Za a xaga matsayin Makarantar Haxa Magani ta Zariya, kuma za a qara yawan ma'aikatan Makarantar Asibitin Kano.

An ajiye kuxi don ginin Haxaxxen Asibitin Okene, tare da Mishan na Roman Catholic. Sabon Asibitin nan da shi da Asibitin Xori na Kano, duka za a fara aiki da su bana.

A cikin ayyukan da ke qarqashin Ministan Al'amuran Cikin Qasa, shekaran nan za ta ga farawar aikin qara buxa Kwalejiin 'yan Sanda – abin da yake wajibi ne wajen horarwan nan ta hanyoyin aiki, da gwamnati ke son ganin ana bayarwa ga 'yan Doka. Haka kuma horon nan da Wuraren Aikin 'yan Sanda na Larduna ke bayarwa ga 'yan Doka, shi ma za a qara tsananta shi.

Cikin shekarun nan goma na baya, ko yaushe ana qara ganin shaidar cewa Dokan nan ta Qasa da Haqqoqin Mutanen Qasa a halaye da dama ta kasa biyan buqatun nan na yanzu, kuma cewa lallai ana buqatar wata sabuwar doka. Don haka ana nufin matsawa, cikin shekaran nan, da aikin bayyane manufan nan, da shirya sabuwar dokar.

Wasu En'e-En'e da damasun kawo shawarwari a riqa rubuta duka takardun iznin riqon qasa da aka bayar a cikin rajista. To, gwamnatina za ta duba hanyoyin yiwuwar haka, ta kawo hanyar nan ta yin rajistar izinin riqon kowace qasa a duk inda, da kuma lokacin da, ya dace.

Ma'aikatar Safiyon Nijeriya ta Arewa za ta ci gaba da shirinta na taswirori, ana kuwa fatar cewa kafin qarshen shekaran nan za a buga sabbin taswirori na zamanin yanzu, na Qasashen da ke tsakanin Katsina-Keffi-Yola-Gaidam, da kuma gavar Arewa. Duka taswirorin nan za a shirya su ne bisa hoton da aka xauka ta jirgin sama.

Akwai manyan tsare-tsaren garuruwan Kano da Kaduna da sauran manyan garuruwa waxanda yanzu a ke cikin yi. Ana kuma fatar cewa shekara mai zuwa za ta zo da qarin Ma'aikatan Tsarin Garuruwa don su iya tasam ma matsalolin nan na Jihar nan da ke qara yawa, na sha'anin raya birane.

Za a ci gaba da ba da kaimi ga qara buxa Majalisun En'e gwargwadon buqata, kuma bisa yadda ya dace da kiyayewar iko da kuma kyakkyawan Mulki.

Game da kuxaden Baitulmalan En'e zarafin nan na raya qasa na bayan yaqi yanzu yana kusa da qarshe. Kuxaxen Ajiyar da aka tara a da, da kuma taimakon kuxi daga hanyoyin waje, sai qafewa su ke yi. Lokaci ya zo da kowace En'e za ta sake duba hanyoyin samun kuxinta, na manyan ayyuka da na yau da kullum, kuma ta tattara duk ayyukanta na raya qasa don kyautata zaman jama'a da arziqin qasa, na cikin shekarun nan goma da suka shige. Idan jama'a na son ci gaba da moriyar ayyukan nan, to, dole ne su shirya biyan kuxin riqonsu, da qara buxa su, daga cikin aljifansu.

A'Larduna da yawa, na quryar Arewa da na Bakin Koguna, an furta jin tsoro bisa yadda dangantaka za ta zama nan gaba tsakanin gwamnatin Jiha da En'e-En'e. To, ina son duk masu irin wannan tsoro a zukatansu su karanta tabbatarwar manufan nan, da kyau, wadda Firmiya ya yi ran 7 ga Disamba na bara. Bari na juyo wani abu kaxan daga cikinta:"gwamnatin Jiha tana sake tabbatar da imaninta ga ginshiqan nan na mulkin dimoquradiyya, su ne qarfin ikon shari'a da 'yancin yin shawarwari, kuma ta xaukar wa kanta alqawarin kiyaye su, sau da qafa. Musamman, ta quduri aniyar za ta xauki En'e-En'e duka dai-dai da juna, ba tare da duban irin karkatar siyasarsu ba, za ta tsaida gaskiya sosai tsakaninsu, ba tare da nuna fifiko ba, kuma za ta guji aikata kowane irin aiki wanda za a iya xukarsa kamar nuna son zuciya ne wajen sha'anin siyasa. Don haka En'e-en's su kwantar da ransu kan cewa, muddin dai su kansu sun tafiyar da alhukkansu da doka ta xora masu, da kuma na maslahar jama'arsu, gwamnatin Jiha ba za ta riqa sa masu baki, cikin zarafinsu, ko kuma ta xora tasirinta a kansu, ba gaira ba dalili ba.

Xaya daga cikin manyan ayyukan Ofishin Ministan Mulkin En'e, shi ne aiwatar da manufan nan ta kafa Hukumomin Larduna wadda Majalisun Jihar nan suka yarda da ita bara. Ana fatar a kawo shirin Dokar Kafa Hukumomin Lardunan nan, a shekara mai zuwa.

Ofishin Ministan Al'amuran Kamaru ta Arewa, zai ci gaba da ingiza da kuma taimakon duka hanyoyin raya Qasar nan ta Amana, tare da haxa kai da sauran Ofishin Ministocin da ke da ayyukan nan.

A wajen Aikin Tarbiyya, babban qoqarin gwamnati za a ci gaba da mai da shi wajen qayyada bazuwar iskancin qananan yara, musamman a alqaryu. Za a qarfafa wa En'e-En'e su kafa Gidajen Tsaron Yaran Iska a biranensu. Kuma su riqa yin amfani da hanyar nan ta danqa yara ga wurin tsaro, a qasashen da ke da ma'aikatan Tarbiyya waxanda za su riqa lura da su.

Za a ci gaba da qarfafa Jam'yyun Gama Kai, bisa hanyar yaqi da matsalolin nan na ba shi da jinginar da kayan gona tun kafin girbi.

Nufin gwamnatina ne ta ci gaba da qarfafa ayyukan raya Sana'o'in qasa waxanda za su taimaka wajen vullo da hanyoyi daban-daban na samun arziqin qasarmu. Harkokin Ofishin Ministan Fidaburdi su ci gaba iyakar gwargwadon matuqar ma'aikatan da suke da su.

Manyan gine-gine da za a fara bana, harda masomin farko na sabon Asibiti a Kaduna da babban Xakin Kimiyya mai bene uku a wurin aikin Binciken Gona na Samaru, da kuma sabuwar Makarantar Gona a Kabba. Banda wannan kuma, ana fatar fara aikin sabon Xakin Shawara na Majalisa, da Gidan Firimiyana Jiha, da Kotunan shari'a na Kano, da ginin ofisoshi masu bene huxu don Hukumar Aikin gwamnati, da kuma Ofishin Baryar En'e a Kwalejiin 'yan Sanda ta Kaduna.

Za a ci gaba da aiki kan qare qaren ayyukan Famfo a Kaduna a Zariya da Jos, kuma ana fata famfon Maiduguri da Katsina za su fara aiki cikin shekaran nan.

gwamnatin Jiha za ta ci gaba da matsa manufar nan ta ba da ayyukan Arewa ga 'yan Arewa, da duk iyakar qarfinta.

Majalisar Kulawa da Sha'anin Sarakunan Jihar Arewa, wadda aka ba da shawarwari kafawa a Taron Gyaran Shirin Mulki da aka yi a shekarar 1957, za a kafa ta nan da nan da zarar an yi gyare-gyaren da suke wajibi ga Shirin Mulkin nan. Majalisan nan za a yi ta da Firimiya, da Sarakunan da ke cikin Majalisar Gudanarwa, waxanda ba za su kasa biyu ba, kuma ba za su shige huxu ba, da kuma wasu Sarakuna guda huxu da za a zave su daga cikin Mashawartan Majalisar Sarakuna. Ni ne zan zama Shugaban Majalisan nan, bisa muqamina na Gwamna. Majalisar ita ce za ta yanke duka al'amuran da suka shafi naxa Sarakuna da yarda da naxinsu, da ba su darajar muqaminsu, da tuve su, da kuma kau da su daga wani wuri na Jihar nan zuwa wani wuri daban cikin Jihar.

A qarshen Jawabin nan nawa, dole ne in koma ga matsalan nan da Sir Bryan Sharwood Smith, gwamnan da na gada, ya ambata a cikin Jawabinsa gare ku na bara. Shi ne kiyayewar amana da amincewa, a lokacin nan na juyin sha'anin siyasa cikin sauri, tsakanin jama'ar qasa da masu iko, tun ma ba kamar Sarakuna da masu riqe da muqamin sarautu ba, waxanda suka sami muqamin nan nasu ta hanyar al'ada, ba ta hanyar zaven jama'a ba. A cikin watannin nan goma sha-biyu na baya, duka En'e-En'e sun mai da kansu ga matsalar

nan, ta hanyar sake duba ma'aikatunsu da kashe duka miyagun abubuwan da ake aikatawa. Ko da yake dai an yi aiki mai amfani ainun, dole ne in qarfafa cewa aikin nan wajibi ne ya zamo sannu sannu kuma mai wahala, don haka har yanzu akwai abubuwa da yawa da suka rage a yi. gwamnatina ta tabbata da muhimmancin, da kuma gaggawar, wannan aiki, kamar yadda gwamnatin da, ta yi. En'e-En'e manyan rukunai ne wajen tafiyar da mulkin, da kuma kyautata, Jihar nan. Kuma ba kururutawa ba ne, a ce idan har En'e-En'e xin nan suka kasa aikinsu, ba shakka dukkan al'amuramnu na nan gaba za su dagule. Saboda haka, yanzu, a goshin samun Mulkin Kai, ya fi ko yaushe zama wajibi, a matsa ci gaba da aikin nan da aka fara bara, na sake shirya duka tsarin hukumomin Mulkin En'e, a gyara wuraren da suka yi rauni, a dai-daita su da buqatun zamani. Wannan aiki ne wanda ku da duka waxanda suka gaji maqaman iko, kuke da alhakkinsa ga jama'ar da kuke mulki da su, da gwamnatin Jiha da gwamnatin Tarayya, da kuma babbansu duka, ga Ubangiji wanda zai tambaye ku wannan amana mai Tsarki da ya danqa muku.

Sarakunan Jihar Arewa, ina roqon Allah Ya sa shawarwarin nan naku, cikin shiriyar Ubangiji, su zama na hikima ne, da rashin son zuciya, da tsinkayar gaba, da kuma tabbataccen amfani ga jama'ar Arewa; Amin.[1]

Aran 16 ga Fabrairun shekarar 1959, Sir Gawain Bell ya yiwa 'yan Majalisar Wakilai jawabi a dab da zuwan lokacin samun Mulkin Kan Jihar Arewa. Mai girma Gwamna ya ce:

Shugaba da Mashawarta.

Wannan shi ne taron qarshe na Majalisar nan kafin Jihar nan ta samu mulkin kanta. Saboda haka nake son in ambaci canje-canje waxanda suka gudana bayan jawabin da na yi maku bara. A Taron da aka yi a London don Shirin Mulki ya yarda a ba Jihar nan mulkin kanta ran 15 ga Maris bana, kuma gwamnatin Tarayya ta samu mulkin kanta ran 1 ga Oktoban shekarar 1960. Waxannan abubuwan alfahari ne gare mu duka. Muna kuwa cikakkiyar godiya saboda kawowa ga wannan matsayi na tafarkin Shirin Mulki a cikin aminci da zumunta. gwamnatina tana sane da dukkan nauyin mas'alolin da suke gabanmu; ku kuma an yi muku bayanin manufar mulkin kai a

---

[1] AH/SNP/20: *Jawabin Mai girma Sir Gawain W. Bell ga Majalisar Sarakuna a ranar 17 ga Maris, 1958, shafi 5-8*

cikin Takardar Bayani ta gwamnati (White Paper) wadda aka kawo gabanku har aka yi mahawara a kanta bara. Galibin shawarwarin da aka bayar a cikin wannan takarda an yarda da su a Taron Tsarin Mulki. To, ga shi yanzu mun doshi wannan babban al'amari; saboda haka niqe roqon Allah taimakon sa da kiwon sa garemu a cikin lokacin de ke gabanmu.

Don tunawa da samun mulkin kai gwamnatina ta yi shirye-shirye na haxa bikiko ina a cikin wannan Jiha. Daga baya kuma, cikin watan Mayu za a ci gaba da shagulgula, waxanda suke har ma Mai Alfarma Sarauniya, cikin karimcinta, ta yarda Masu Xaukaka, Duke na Gloucester da unwargidansa su wakilce su.

Kafin in zana shirye-shiryen gwamnati domin shekara mai zuwa, na ga ya kamata in maimaita manufar gwamnatina ga abubuwa biyu muhimmai. Su ne, hukuncin shari'a da ba 'yan Arewa ayyukan gwamnati. Da farko dai, gwamnatina ta xauka cewa kafa hanyar hukunci wadda ba ta qarqashin kowa, ba ta yarda da son zuciya ba, kuma za a yarda da ita a sauran daulolin duniya ya fi komi zama muhimmin abu gareta. Don a samu haka, gwamnati ta shirya ta kawo Shirin doka bana, wadda za a ciro qa'idodinta daga cikin shawarwarin da ke cikin Takardar Bayanin gwamnati a kan gyaran hanyar hukunci da dokoki, wadda aka kawo gabanku a watan Disamba wanda ya wuce. Na biyu, gwamnati ta yi yaqini da buqatar hanzatar da ba 'yan Arewa ayyukan gwamnati. Saboda haka gwamnati ta kafa wani Kwamiti wanda zai ba ta shawara a kan kowace fuska ta game da tafiyae da ba 'yan Arewa ayyukan gwamnati. Ministan shi ne Shugaban wannan Kwamiti. An shirya kuma a ba wannan Kwamiti ma'aikata nasa daban kuma a danganar da su a Ofishin Firimiya. Ko da yake gwamnati na son ta kora wannan muradi da himma ainun, amma duk da haka tana son ta warware wa ma'aikata waxanda ba 'yan Arewa ba cewa ana matuqar maraba da su kuma ba za a nuna masu son rai ba domin bambancin qabilarsu, ko abin da suka yi imani da shi, wurin haifuwarsu.

Yanzu kuma mu koma ga sha'anonin gwamnati na kullum. Ga shi kuma mun sake kawo lokacin da ake roqonku ku duba lissafe-lissafen kuxi ku kuma ba da kuxin da gwamnatina take buqata don ta zatar da shirye-shiryanta na shekara mai zuwa ta kuma daidaita linzamin mulki. Ministan Kuxi zai gabatar da Dokar Kasafin Kuxin shekara, wadda ke da Azuzuwa talatin da huxu na kuxin kashewa yau da kullum, da jimillar kuxi kusan fam miliyan goma sha-biyar cikinsu. Wannan jimillar ta hada da kuxin da za a kashe don Bukin Samun

Mulkin Kai ta cikin watan Mayu. Bayan wannan kuma an shirya kashe fiye da fam miliyan takwas a wajen lissafin kuxi na Manyan Ayuka. Jawabin Ministan Kuxi a kan Istimat zai kawo bayani na al'ada game da sha'anin kuxin Jihar nan da wadatarta.

Bana gwamnatina tana son ta nemo rance har na fam miliyan biyu da rabi don jarin da za a yi amfani da shi wajen ayyukan raya qasa. Daga wannan jimilla miliyan huxu da rubu'i za a nemo su daga gwamnatin Tarayya a bisa qa'idodin Dokar Neman Rance ta shekarar 1958, saura miliyan xaya kuma za a ranto daga Hukumar sayar da kayan gona ta Jihar Arewa.

Koda shi ke gwamnati na za ta ci gaba da zartar da muradinata game da ba 'yan Arewa aikin gwamnati a kowane matsayi, kamar yadda na riga na ambata, duk da haka tana da cikakken sanin cewa muhimmin abu ne a kiyaye zaman ma'aikatanta na yanzu. Hasali dai, ana fata shawarorin da wazirin Ingila Mai kula da Qasashen waje ya bayar, waxanda kuma ita gwamnati ta karva, za su qarfafa zukatan ma'aikata waxanda ba 'yan qasa ba har su ji daxin ci gaba da aikinsu cikin wannan Jiha bayan samun Mulkin Kai. Amma waxanda suka zabi barin aiki an shirya kuxi fam dubu xari biyar don biyansu dunqulalliyar diya a cikin shekara mai zuwa. Waxannan qudi za a biya su daga Istimat na kuxin aikin Yau da Kullum za a kuma same su daga cikin kuxin da gwamnati ke samu yau da kullum.

Bayan Shirin Dokar Kasafin Kuxin Shekara, Ministan Kuxi zai kuma kawo waxansu dokoki. Za a kawo Shirin Dokar Qarin Kasafin Kuxin Shekara domin Qarin kuxin da ake nema a kashe cikin wannan shekara. Za a kuma kawo Shirin Dokar Harajin Jiha. Manufar wannan Shirin Doka ta dai-daita hanyar harajin Jiha da zamani, ta kuma ingantata. Za a kuma kawo dokoki don gabatar da haraji a wasan sinima da sukuwar dawaki da cacar mashin da ta duro waxanda a ke yi a wajen sukuwar dawaki. Za a kuma gabatar da Shirin Doka domin kawo gyare-gyare a Dokar Mallaka da Tafiyar da Sha'anin Kuxaxen gwamnati ta 1958.[1]

Wani abin da za a yi la'akari da shi, a lokacin mulkin waxannan Gwamnoni, shi ne an ba ilimi da sana'a muhimmanci sosai. Dalilin haka ne ma, Mai girma ya yi bayani da cewa:

---

[1] AH/SNP/SA A21/ *Jawabin Mai girma Gwamna Sir Gawain Bell ga 'yan Majalisar Wakilai a ran 16 ga Fabrairu 1959, shafi 1-2*

Ilimin sana'o'i, manufar gwamnati shi ne za a gina makarantun sana'a uku kafin qarshen shekarar; a lokacin nan zai zama akwai yara dubu da xari biyu waxanda su ke samun irin wannan . Abin shakka guda ne ko za a samu isassun ma'aikata. A bana an rage ayyukan makarantar sana'a ta Kaduna da kuma maida waxansu ayyukanta zuwa makarantar Sana'a babba ta Ilori zai ba da wuri domin a koyar da ilimin manyan sana'o'i. Wannan ya kawo wani irin tsari a cikin Afirka ta Yamma game da Babbar Takardar Shaidan ta London City and Guilds wadda babu shakka za ta zama manufar shirye-shirye ta ba da waxanda za a kawo su a makarantar sana'a nan gaba. Ban yi tsammanin za a yi wani babban abu ba game da ilimin 'yan mata da na mata, amma ma'aikatar Ministan tana da niyya duk da haka ta yi iyakacin yadda ta ga ra'ayin jama'a da kuma samuwar ma'aikatan da suke da su za su bari. Haka kuma ba ni ba da wani alqawari da zan yi game da ci gaban Yaqi da Jalhici, ko wayewa jama'a duhun kai. Amma nan kuma an yi shirye-shirye wanda za a yi aiki da su a lokacin da aka ga ra'ayin jama'a ya karyo nan. In mun juya wajen aikin magani da kiwon lafiya gwamnatina ta yi niyya ta ci gaba da sauri wajen koyawa ma'aikata aiki a kan kowace fuska ta wannan aiki. Kashi arba'in da biyar daga cikin xari na ma'aikatan wannan ma'aikata waxanda ba su cikin ainihin aikin maganin dukansu a yazu 'yan Nijeriya ne san nan kuma akwai shiri na a kara yawan kimanin 'yan Nijeriya a cikin waxanda suke suna cikin aikin kiwon lafiya.

Za a miqawa Ma'aikatan Ministan Makaranatar Koyon Aikin Magani ta Kano domin su riqa koyawa yara karatu domin su xauki Takardar Shaida ta (School Certificate na G.C.E. Advance Level) a cikin ilimin Kimiya domin ta haka za a samu Qarin yawan 'yan makaranta waxanda za su iya shiga makarantu na aikin magani a cikin Nijeriya da kuma qasashen waje. Amma mataimakan likita za su ci gaba da koyonsu a makarantar har su qarasa.

"A wajen aikin Nas a bara an xauki Nas shida domin su je koyon aiki a Ingila, su samu takardar shaida ta Ingila takan wannan zai sa jimillar dukkan Nas Nas da suka koyo aiki a Ingila ya zama ashirin da uku sa'an nan akwai shiri da aka yin a xaukar Nas domin koya masu a Ingila kowace shekara. A Kaduna Makarantar Koyon Nas da wurin kwanansu an kusa gama gininsu, ana kuma fata Mai Daraja Uwargidan Duke na Gloucester za ta buxe ta a lokacin zuwansu wannan Jiha domin bikin samun Mulkin-Kai a cikin watan Mayu. Idan aka fara aiki a wannan makaranta yawan Nas da ake koyawa

aiki a kowace shekara zai qaru kimanin rabi. An kuma yarda da kafa makarantu na koya aikin unguwar zoma masu daraja ta biyu a asibiti guda bakwai na cikin Jiha; za a fara koyar da aiki a cikinsu a bana har ma zuwa gaba zai yi amfani qwarai wajen rage qarancin ma'aikatan unguwar zoma wanda yanzu yake hana qara girman asibitoci da aikin magani a qauyuka. Ta haka za a qara yawan masu shiga makarantar aikin Nas ta Kaduna domin a koya masu aiki na unguwar zoma mai daraja ta biyu, waxanda za su yiwa En'e-En'e aikin kiwon lafiyar yara da ziyarar gidaje. Makarantar koya aikin magani ta Kaduna za a qara girmanta da gidan 'yan makaranta xaya da kuma azuzuwa domin a samu damar ruva yawan masu aikin disfensare sau biyu. Bayan wannan kuma za a gina wurin kai mata masu ciki da kuma masu reno a kusa da wannan makarantar wanda zuwa gaba za ta zama wurin da za a iya mayar da shi wurin aikin unguwar zoma masu shiga gida-gida.

Samun qaruwan likitoci da kuma qananan ma'aikata ya sa an sake samun ci gaba da aikin gine-gine har ma ba da daxewa ba za a fara aikin ginin asibitoci uku a Birnin Kudu da Bama da Ganye da kuma sake ginin asibitocin Hadejia, Wukari da Azare. A Ilori asibitin masu ciki an maidai ita a hannun gwamnati yanzu san nan kuma za a yi mata qari kuma da sabunta ta, sa'an nan a gina wurin aikin haqora. A Gombe inda yake dama akwai qaramar asibiti wadda En'e ta gina za a gina sabon daqi mai gado 30 tare da taimakon gwamnati. Za a kuma kyautata ayyukan da ake da su a asibitocin Idah, Lokoja, Makurxi, Ilori, Mubi, Bida da Bauchi idan aka kai masu lantarki wanda zai ba da damar a sa masu abin daukar hoto. A Kano kuma Asibitin Xori yanzu an gamata za a kuma buxe ta a cikin watan Afrilu.

Amma duk da haka, wannan ba zai sa a manta da buqace-buqacen qauyuka ba. Ma'aikata na aikin asibiti na Majalisar duniya da aikin kula da yara masu aikin (yaws) sun kai lardin Wukari; a cikin shekara mai zuwa za su qetare kogin Binuwai su ci gaba da aikinsu na tafiya zuwa Yamma a bakin kogin Gabas cikin qasar Lafiya da Nassarawa sai sun haxu da masu aiki waxanda suke sake bincike a cikin qasar Abuja. Duk da haka kuma akwai waxansu ma'aikata za su ci gaba da aiki cikin qasar Igala, Idoma da ta Tiv domin su tsare wurare inda suke akwai qungiya-qungiya ta cuta. A Yammacin Sokoto masu aikin kiwon lafiyana Majalisar duniya da kuma masu aikin kula da yara da suke aikin ciwon massasara wadda take ta yaxu wa cikin yankin qasa wanda yawancin shi ya fi murabba'in mil 6,000 kuma akwai mutane wajen dubu xari biyar

500,000 cikinta, za su ci gaba da aikinsu. Sa'an nan za a nemi taimako daga sauran qasashen duniya domin a tabbatar da irin nasarar da aka riga aka samu, zuwa gaba kuma a qara yawan wurin da ake baza wannan yaqi. A Kaduna kuma ba daxewa ba za a kafa wurin aikin bincike na Jiha domin ciwon masassara wanda zai ba da wurin aiki na bincike da kuma koyarwa waxanda ake buqata domin a ci gaba da wannan yakin.[1]

Saboda gabatowar lokacin samun 'yancin Tarayya sai aka yi qoqarin hanzarta gama ayyukan da a ke yi don a hanzarta kammala su wannan ya sa gwamnan ya yi nuni da:

Ana samun ci gaba mai yawa wajen shirin yaxa hanyoyi waxanda ake tsammanin za a gamasu a cikin watan Satumban shekarar 1960. Akwai shiri ashirin da xayana aikin hanyoyi da yanzu ake tafiyar da su a wurare daban-daban cikin Jiha. Ana kuma shirin kwangilar aikin gyaran gadoji ashirin da bakwai a cikin lardin Neja. Sa'an nan kuma akwai kwangila uku waxanda aka yi tallarsu, ga shi kuma nan gaba ba da daxewa ba za a kawo tallar biyu.

Za a ci gaba da aikin hanyoyin gwamnatin Tarayya har game da gyaran gadoji a hanyar Ilori wadda ta biyo ta Kontagora da Kaduna da Zaria da kuma hanyar tsakanin Gusau da Sokoto.

Za a ci gaba da shirye-shirye na koyawa ma'aikata aiki a Ma'aikatar Ministan Ayyuka. Za a fara aiki domin yin shirin yadda za a sa wayar lantarki cikin gine-gine gwamnati a garuruwa waxanda a ke son a kai masu lantark. A cikin waxannan garuruwa Ilori ita ce ta farko.

Aikin ba da ruwa a qauyuka zai ci gaba da qarin kuxi da aka yi domin shi shirin da aka yi da farko na shekara biyar har an qare shi a cikin shekara huxu. Za a ci gaba kuma da ginin rijioyi a kusa da Tabkin Chadi da kayan Ma'aikatar da kuma taimakon yan kwangila, inda ya zama dole. Ana fata a kai ruwan famfo a Bama, Gumel, Kabba, Kura da Yelwa cikin wannan shekarar.

Ana fata kuma qarin aiki da ake yi na famfon Jos da Zaria a qarasa shi. Za a kuma ci gaba da qarin aikin famfo a Kaduna da Kano. Kafin in qarasa, Shugaba, da 'yan Majalisa, ina roqon Allah Ya qarfafa ku cikin ayyukan ku kuma, ya shiryar da ku cikin

---

[1] AH/SNP/SA A21/ *Jawabin Mai girma Gwamna Sir Gawain Bell ga 'yan Majalisar Wakilai a ran 16 ga Fabrairu 1959, shafi na* 5-7

shawarwarinku domin amfanin mutanen Jihar nan. A zamaninsa ne Sarkin Bauci ya sami lambar girma."

Shagalin ba Sarkin Bauci Lambar C.B.E

An yi gawurtaccen taron gaske a Bauci saboda rataya wa Sarkin Bauci M. Adamu Jumba Lambar C.B.E da Mai martaba Sarauniyar Ingila ta ba shi. Takanas gwamnan Jihar Arewa, Sir Gawain Bell, ya tafi Bauci domin rataya wa Sarkin Bauci wannan lamba. A cikin jawabin da Gwamna ya yi yace, "cike nake da nishaxi da farin cikin zuwana Bauci a wannan lokaci domin rataya wa Sarki lambarsa ta C.B.E., wadda Mai martaba sarauniyar Ingila ta ba shi a bana."

Gwamna ya ci gaba da cewa, "Sarkin Bauci ba shakka tun lokacin da ka gaji wannan sarauta taka, ka nuna iya shugabanci, dabara, adalci da cikakken natsuwa cikin tafiyar da sha'anin mulkinka ga mutanenta da kuma ga gwamnati. Qoqarin naka ya zama abin misali ne ga jama'ar ka da dai dukan sauran jama'ar wannan jiha"

Sarkin Bauci, a wajen mayar wa Gwamna da amsar jawabinsa, bayan kyakkyawar godiya ga Ubangiji da yabon Annabi Muhammadu, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

Ina yi wa Gwamna maraba shi da Firimiya, Firayim Minista da Ministocin Jiha, 'yanuwana saraki da 'yam Majalisunsu da dai dukan waxanda suka halarci taron nan na ba ni lamba. Ina kuma bayyana godiya ta ga Mai martaba da ta bani wannan lamba ta C.B.E.

Na gode wa mutanen Bauci dukansu, mazansu da matansu, musamman 'yan Majalisata waxanda da taimakon su ne na sami wannan girma. Nagode wa Hakimai, shugabannin ma'aikatu, Dagatai da dai kukan ma'aikatan En'e, waxanda ta qwazonsu ne, gaskiyarsu a aiki da biyayyarsu suka jawo mini wannan girma. Ko ban faxi ba, na tabbata jama'a sun gane irin gawurtaccen ci gaban da aka yi a Bauci. Nagode wa Razdan da sauran masu aikin mulki da Turawa shugabannin ma'aikatu, waxanda har yanzu mu ke zaune tare da su da kuma waxanda suka riga suka bar mu da qananan ma'aikatan gwamnati, saboda taimakon da suka yi, taimakon da shi ya jawo mana ci gaba a lardin Bauci.

Ba ni iya cewa komai game da ni kaina, amma dai na tabbata ba ni wannan lamba ba kawai mutanen Bauci ne ransu zai yi fari ba, har ma dukan mutanen Jihar Arewa ransu zai yi fari. A qarshen jawabin nan nawa dai, ina roqon Allah Ya taimake ni ya sa in sarauci

mutanena bisa adalci. Ina kuwa fata dukan waxanda suka baro garuruwansu domin wannan shagali, Allah Ya maishe su gida lafiya.

Da Gwamna ya gama ba Sarki Lamba sai aka harba bindiga har sau shida, dirim, dirim, dirim! Daga nan dai Hakimai da Dagatai suka yi wa Sarki jafi. Irin dai shagalin raye-raye da waqe-waqen da aka yi, sai wanda ya gani. Kafin gwamnan Arewa ya baro Bauci, sai da ya yi wa su Sarakunan Bauci, Dass da na Ningi jawabi. Gwamna ya gode musu saboda kyakkyawar marabar da suka yi masa a wannan ziyara tasa ta biyu zuwa Bauci. Gwamna ya ce musu ya yi baqin ciki qwarai da ba zai sami damar ziyartarsu har gidajensu ba.

Gwamna ya tavo batun irin nasarar da aka yi na Taron London da kuma maganar Mulkin kan Jihar Arewa. Ya bayyana cewa kafaffen mulkin En'e da aka gina bisa adalci ga dukan jama'a da rashin son kai, wajibi ne a same shi wajen ginin arziqin jiha. Ya ce, "Saboda haka xaya daga cikin manyan buri, lallai ya zama akwai qarfafa majalisu, don kuwa ta nan ne za a fi jin ra'ayin jama'a. Gwamna ya bayyana cewa ana qoqari qwarai yadda za a sami telefon na rediyo tsakanin Bauci da Jos. Hasali dai Sarkin Bauci a madadinsa shi kansa da madadin Sarkin Ningi da na Dass, 'yam Majalisunsu da jama'arsu, ya yaba wa Gwamna.

Har ila yau kafin mulkin Sir Gawain Bell ya zo qarshe sai da ya halarci Shagalin bikin cika shekara hamsin da Sarkin Daura ya yi a sarauta.

Sarkin Daura Ya Yi Bikin Cika Shekara 50

Sarkin Daura Alhaji Abdurrahaman yana da shekara tamanin da biyu da haihuwa ya yi bikin cika shekara hamsin a kan gadon Sarauta. Shi ne Sarkin da Gwamna Lugga ya naxa na qarshe da ya samu tsawon ran samun shekara hamsin yana mulki.

Sarki Abdurrahman ya yi wannan qasaitaccen biki ne ran 31 ga Janairu shekarar 1962 a garin Daura, mai daxaxxen tarihi. A ranar wannan shagalin biki ne garin Daura ya cika maqil da baqi, manya da qanana. Sarakuna daga dukkan qasashen Hausa Bakwai sun halarci wannan biki. Waxannan manyan baqi sun haxa da Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, da gwamnan Arewa Sir Gawain Bell, shugabanni da wakilai daga dukkan sassan Nijeriya da qasar Nijer.

A wannan rana an yi 'yar qaramar Daba a fadar Sarki inda dawaki dubu da mutum wajen dubu suka yi jafi a gaban Sarki. Wannan Daba ta qawatar da wannan shagali matuqar gaske. A wannan lokaci ne Razdan Mr. E.O.W Hunt, ya karanta saqon taya murna daga Sarauniya Bayan ya gama jawabinsa, sai gwamnan Jihar Arewa ya miqe ya gabatar da nasa jawabin taya Sarki Abdurrahman murnar cika shekara hamsin a gadon sarauta. Ga jawabin Mai girma Gwamna:

Mai girma Firimiya, Sarakuna, Ministoci, Sarki da jama'ar Daura.

Wannan rana ce mai muhimmanci a tarihin Nijeriya ta Arewa, ya kuma dace da ayi shagalin ta da daraja da qawatarwar gaske kamar yadda muka gani. Shagali ne kuma da ya kamata mutane da manyan baqi masu yawa su halarta.

A watan Janairun shekarar 1912 ne Gwamna Lugga ya miqawa wani matashi mai suna Abdurrahman sandar tabbatar da shi Sarkin Daura. Wannan shi ne qasaitaccen mutumin da muka zo yau don mutaya shi murnar samun shekara hamsin akan gadon sarautar Daura. Shi ne Sarkin da ya samu wannan tsawon shekaru a Arewa yana shugabancin jama'arsa.

A zamanin kana Sarki, Alhaji Abdurrahman ka ga yadda Nijeriya ta taso tana ci gaba, tana bunqasa cikin lumana har ta kai ga samun 'yanci. Saboda haka bashin da shugabanni kamarka ke bin mutanen wannan qasa babba ne. A duk lokacin waxannan sauye-sauye sai ka tsaya tsayin daka wajen ciyar da jama'ar masarautarka gaba tare da jama'arta fiye da komai kayi aiki a hankali da kyakkyawan niyya wajen kawo wa jama'arka abubuwan zamani na ci gaba masu kyau tare kuma da qarfafa kyawawan xabi'u da al'adun jama'arka.

Sarkin Daura, kai ne Sarki na goma sha-huxu da Gwamna Lugga ya naxa, ina mai farin cikin taya ka murnar samun shekara hamsin a karagar mulki. Na yi imani da cewa ina faxin abin da ke cikin zukata jama'a masoyanka da ke wannan waje da waxanda basa nan musamman waxanda suka daxe da barin Nijeriya bayan sun bar aiki, sun yi ritaya. Ina roqon Ubangiji da ya qarawa jama'arka shekaru masu yawa na zaman lafiya da farin ciki a qarqashin shugabancinka da kuma jagorancinka na uban al'umma.[1]

Gwamna na gama jawabinsa sai Sardauna ya miqe don ya gabatar da nasa bayanin. A cikin jawabinsa Sir Ahmadu Bello ya ce babu shakka mutanen Daura za su yadda da cewa sun yi sa'a da suka sami hikimar jagoranci da shugabancin Alhaji Abdurrahman. Ya cewannan Sarki ne da ya gane wa idonsa tarihin Nijeriya. Sardauna ya cewannan abu ne da yake buqatar hikima, juriya tare da son jama'a wajen daure wa, waxannan canje-canje da suka faru a wannan qasa, waxanda ka iya kiximar da wanda ya yake ba gwarzo ne ba.

A qarshen jawabinsa sai Firimiya ya bada sanarwar cewa asibitin da ake shirin ginawa a Daura, za a sanya masa sunan Alhaji Abdurrahman don a qara tunawa

[1] N.C/No 1009, Laraba 7/2/1962

da gudunmawar da wannan mashahurin Sarki ya baiwa jama'arsa da kuma wannan qasa baki xaya. Daga nan sai ya miqa wa Sarkin kyautar takobi mai adon zinare da azurfa don tunawa da wannan biki.

Daga nan sai Mai girma Sarkin Daura ya miqe don ya mayar da jawabi. Ya fara da godewa Allah da ya bashi tsawon rai da qoshin lafiya har yaga wannan rana. Ya kuma godewa duk waxanda suka sami ikon halartar wannan biki ko suka turo wakilansu. Sarkin sai ya miqa godiyarsa ga Mai martaba Sarauniya, da Gwamna Janar na Nijeriya, da Firayim Minista da Kuma Firimiya wanda ya yabeshi wajen mulki da adalci.

Bayan Sarki ya gama jawabinsa sai Gwamna da Firimiya da Sarakuna tare da sauran manyan baqi suka tafi wajen nunin kayan tarihin Daura. A cikin abubuwan tarihi da aka nuna har da wuqar Bayajidda, da wasiqar naxa Sarki Abdurrahman wadda Gwamna Lugga da Gwamna Janar suka sanya hannu ran 2 ga watan Yulin shekarar 1912, da Alkyabbar Sarki ta farko.[1]

A qarshen mulkin Sir Gawain Bell, sai da ya ziyarci lardi wasu larduna a Arewa domin bankwana da shugabanin da jama'arsu saboda Gwamna ne da ya shimfixa ayyuka masu yawa ya kuma halarci bukukuwa iri-iri, manya da qanana a duk faxin wannan Jiha.

Bankwana da Sir Gawain Bell a Kano

gwamnan Arewacin Nijeriya Sir Gawain Bell, ya ce yana cikin baqin cikin zai bar Arewa nan gaba kaxan, sai dai ya ce cike yake da alfaharin zai bar Arewa qarqashin jagorancin Sir Ahmadu, da kuma nasarar da ya samu a lokacin da yake a nan.

Mai girma Gwamna na mayar da jawabi ga jawabin bankwana da Sarkin Kano Alhaji Sir, Muhammadu Sanusi ya gabatar masa a ranar Alhamis ne lokacin da ake bankwana da shi. Sir Gawain Bell tare da Lady Bell da Ministan Yaxa Labaru Alhaji Ibrahim Biu (a madadin Firimiya) sun isa Kano ta jirgin sama domin rangadin bankwana da Lardin Kano da Katsina da Sokoto.

A kan Kano gwamnan ya ce: Akwai 'yan xaixaikun (birane 'yan qalilan) a duniya da za su iya cewa tarihinsu ya kai shekara dubu, sai 'yan xaixaiku da zu su ce suna da tarihi a rubuce na Sarakuna arba'in da takwas da suka yi zamani a lokuta daban-daban. Kano na bunqasa tana aiki da rodi da cinikin bani manda in ba ka gishiri da Arewacin Afirka tun zuri'a xaya bayan xaya har guda hamsin. Ya yi bayanin cewa waxannan al'adu ba qananan abubuwan abin alfahari ba ne; ko a yau, Kano cibiya ce ta masana'antu da cinikayya ta Arewa.

Da yake batu akan Kano a matsayinta na cibiyar neman ilimin Mai girma gwamnan ya yi fatar kafa kwalejin Abdullahi Bayero, garin zai zama xaya daga

[1] N.C/No 1009, Laraba 7/2/1962

cikin cibiyoyin da ke kan gaba a duk faxin Afirka ta Yamma vangaren karatu. Sir Gawai ya ce: "Kafa Hukumar tsara Kano ko shakka babu ba za a daxe ba wannan birni zai zama abin misali na abubuwan more rayuwa irin na zamani da kyakkyawan tsari na fulotai."

A qarshe Mai girma ya tavo matsaloli da ci gaban zai kawo tare da qarin bayanin cewa, "Na yi imani cewa ta hanyar adalci da yi wa jama'a aiki, da ci gaban haqqoqin jama'a da tinqaho da alfahari na al'ummarta, Kano da masarautar Kano za su zama kyakkyawan abin koyi ga dukkan 'yan Nijeriya."

Tunda farko a jawabinsa Sarkin Kano ya kwatanta tafiyar Gawain da Uwargidarsa a matsayin abin baqin ciki. Ya yi nuni da cewa, Sir Gawain ya iso qasar nan a wani mawuyacin hali amma saboda dagewarsa, da qwazonsa da kyakkyawan jagora, ya iya gudanar da aikinsa ba tare da wata matsala ba. A qarshe Sarkin ya ce: "Biyayyarka da iya abotarka da haxin kan da ka bayar, za su daxe a zukatanmu bayan tafiyarka."

A madadin shi kansa da jama'arsa yana yi wa Mai girma da Uwargidansa fatar alheri a lokacin ritayarsa, da tsawon rai da lafiya da ci gaba. Daga bisani, Mai girma Gwamna tare da rakiyar Sarki sun shiga mota cikin dogon jerin gwano zuwa masauki inda Sarkin ya yi bankwana da Gwamna. Gwamna tare da Uwargidansa da baqi masu xan yawa ciki har da Ministan yaxa labaru, sun halarci wata 'yar qwarya-qwaryar liyafa a masaukin gwamnan da rana kafin ya shiga jirgi zuwa Katsina domin ci gaba da rangadin nasu.

Tunda farko da ya isa filin jirgin sama na Kano kafin ya duba faretin girmamawa da 'yan Sanda En'e suka yi, Sarki ya sadu da gwamnan, da babban Razdan na Kano Mr. N.F. Cooke, da mataimakin Kwamishinan 'yan Sanda Mr. N.V.B. Willmshurt; da mai shari'a Mr. Bale da uwargidarsa; da Sarkin Haxeja, da na Gumel, da Kazaure, da Kansilokinsu, da S.D.O. na Kano (babban D.O) Mr. D.A. Thain.[1]

Bankwana da Gawain Bell a Katsina

Sarkin Katsina, Alhaji Sir Usman Nagogo, ya kai gagarumar jinjina ga gwamnan Arewa, Sir Gawain Bell saboda gudunmawar da ya bayar ga ci gaban yankin da kuma qasa baki xaya. Sarkin Katsina ya ce al'amuran tarihi masu yawan gaske kamar su samun 'yancin kai na yanki da 'yancin kan Nijeriya sun gudana a shekaru huxu da rabi da Sir Gawain Bell ya yi yana kan mulki. Ya ce shi dai jama'arsa suna alfaharin cewa Arewa ta yi sa'a da ta samu Sir Gawain a matsayin gwamnanta da Sir Ahmadu a Bello a matsayin Firimiya, saboda su mutane ne da ke da qwarewa ta siyasa da iya gudanar da Mulki. Ya yaba wa gwamnan saboda xaga matsayin boko a yankin.

---

[1] NC, Lamba, 1,041, Laraba 6/6/1962

Sarkin ya kuma jinjinawa gwamnan yankin saboda abin da ya kira tsare-tsarenta na ci gaba, da miqewa tsaye da ta yi wajen gudanar da wani gagarumin tsarin ci gaba na shekaru shida. Ya qare jawabin nasa da cewa: "Muna masu ba ka tabbacin goyon baya da cikakkiyar biyayyar Majalisar mu ga Firimiya Sir Ahmadu Bello da gwamnatinsa. Da yake mayar da jawabi, gwamnan ya ce:

Sarkin Katsina, da Sarkin Daura, da masu Girma Ministoci da Kansiloli, bari in soma da gode maku saboda jawabinku na bankwana, kuma zan iya cewa gagarumar dama ce na zamana tare da 'yan Nijeriya a ci gabanta zuwa samun 'yancin kai, da kuma yin aiki da Sarakuna da Shugabannin Arewa. Zan koma Ingila cike da farin ciki da alfahari na farin cikin abubuwan da zan iya tunawa na aikin da na yi a nan.

Abin farin ciki ne da jin daxi in aka lura da sauye-sauyen ilimin da aka samu cikin hanzari a 'yan kwanakin nan a yanayi na ba a san ya gobe za ta kasance ba, domin kuwa mun dogara ga qarfin al'adunmu da ya sanya muka iya xora yanzu a kan kyakkyawar turvar da take akai a yanzu. Saboda dogon tarihi da kyawawan xabi'un al'adunku, kuna da babban abin tunqaho, wato qwaqqwaran tubalin ginin al'umma.

Ba qaramin abu ba ne ya zama muna da wani tarihin da za a yi alfahari da shi, sa'an nan a ci gaba da shi a lokuta da ke canzawa kamar yadda kuka yi shi ne mafi dacewa. Kai Mai martaba Usman da kai Mai martaba Sarkin Daura kun yi nasara a wannan ci gaba, kuma a lokaci guda kuka yi abin da ya dacewajen kare dukkan hanyoyinku na rayuwa a al'adance. Ina taya ku murna.

Bai kamata in kwatanta wani lardi da wani ba. Domin kuwa na yi matuqar jin daxin rangadin da na yi a dukkansu. Sai dai ina jin zan iya cewa, a lokacin da na ziyarci Katsina da Daura na yi sa'ar da kaxan ya rage in nemi hutu don hutawa a can domin ganin ko zan yi 'yar farautar ko hawa a xaya ko a duka garuruwan. Zan dinga tunawa da ina bin makwarwa a wajen garin Daura; zan kuma tuna sanyin safiya ina tsaye a tafkin Mani ina jiran agwagwa, da rana kuma ina filin Polo na Katsina. Kuma wa zai mance da nasara da tsoho ya samu a kan matasa a watan Fabrairu da ya gabata.

Sarkin Katsina, Sarkin Daura, da masu Girma Ministoci da Kansiloli, zan koma da waxannan abubuwa da ba zan tava mancewa

da su ba, kuma zan ci gaba da duba ci gaban da kuke samu cikin farin ciki."Sai wata rana Allah Ya bamu lafiya da tsawon rai.[1]

Tun farko da ya isa fadar Sarki a safiyar xaya ga watan Yunin shekarar 1962, gwamnan ya duba Faretin ban girma da 'yan Sandan En'e ta Katsina suka yi kafin Mai girma ya bar fadar, sa'an nan suka suka kaxa masa kixan ban kwana da Hausa. Sir Gawain Bell tare da Ministan yaxa labarai Alhaji Ibrahim Biu daga bisani sun shigo jirgi zuwa Sokoto domin ci gaba da rangadin bankwana. Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sokoto ya bar Kaduna ta jirgin sama a safiyar Jumma'ar da ta gabata domin zuwa Sokoto ya iske Gwamna, Sir Gawain Bell da Uwargidansa Lady Bell a rangadin bankwana da suke yi na lardin.[2]

Bankwana da Gawain Bell A Sakkwato

A ran 2 ga Yunin shekarar 1962, Gwamna mai ritaya ya isa Sakkwato a ziyararsa ta bankawana da Arewa. Firimiya ya baro Kaduna zuwa Sakkwato don ya taya gwamnan wannan ziyara. A wannan lokaci ne Sir Gawain Bell ya isa Fadar, Sir Abubakar wanda ya yi jawabin barka da zuwansa. A cikin jawabinsa sai Mai martaba ya ce, "muna cike da farin ciki tare da alhini a wannan lokaci da muke maraba da zuwanka saboda wannan shi ne saduwarmu ta qarshe." Sir Abubakar ya yabi gwamnan da xaukar wannan ziyara zuwa kowane lardin Jihar nan.[3]

Ya kuma tabbatar wa da gwamnan cewa shi da jama'arsa za su riqa tunawa da ziyarce-ziyarcen da Gwamna ya yiwa Sakkwato. Haka kuma sunan Sir Gawain ba zai vace ba a tarihin Arewa, saboda a duk lokacin da za a rubuta littafin tarihin mulkin Ingilishi a Arewa, sai an ba da kyakkyawar gudunmawarsa a zamanin mulkinsa a wannan jiha.[4]

Shi kuwa a jawabinsa gwamnan mai ritaya ya ce a kullum zai riqa tunawa tare da farin ciki saboda sa'ar da ya samu na aiki a Nijeriya ta Arewa a lokacin mulkinsa. Ya kuma qara da cewa ya ji daxi matuqa da abotar da ta qullu a tsakaninsa da, da Firimiya. Mai girma gwamnan ya qara da cewa zai zama mai sha'awar ganin ci gaban wannan jiha ne da Tarayyar Nijeriya baki xaya.

Haka kuma ya yabawa shugabannin Nijeriya saboda nuna ladabinsu, da son raharsu da kuma mutunci. Gwamna ya qara da cewa, "matuqar 'yan Arewa suka ci

---

1 NC, Laraba 6/6/1962, shafi na 12

2 NC, Laraba 6/6/1962, shafi na 12

3 *Ibid* . Asabar, 9/6/1962, shafi na 9

4 *Ibid*., Asabar, 9/6/1962, shafi na 12

gaba da riqe addininsu da girmamawa da sanin ya kamata, to, Nijeriya ta Arewa zata ba da muhimmiyar gudunmawa a Tarayyar Nijeriya, wadda ita kuma zata taka rawar gani wajen dawo wa da duniya kirki da nagarta waxanda ta rasa su a yanzu."[1]

Bayan wannan babban baqo ya gama jawabinsa sai ya tafi ya kai ziyara a Hubbaren Shehu, a inda Firimiya da Ministoci guda biyu; Alhaji Ibrahim Biu, da Alhaji Sule Gaya suka yi masa rakiya. gwamnan kuma ya duba ginin da ake yi na masallacin Bello, sa'an nan ya kai ziyara a Babban Asibitin Sakkwato. A wannan asibiti ne gwamnan ya miqawa Malama 'yar Sa'idu takardar shaidar yabo, saboda ta cika shekaru talatin da takwas cur, ta na aiki da En'e ta Sakkwato.

A wannan ziyara ta sa, sai da ya yi tafiyar mil talatin a mota zuwa garin Degel, inda ya kai ziyara ga kabarin Fodio. Haka kuma sai da shi da ayarinsa suka tafi Marnona don su ga kabarin Hauwa'u mahaifiyar Shehu Mujaddadi.

Sir Gawain Bell, mutum ne wanda ilimin musulunci ke ba shi sha'awa saboda kusan a tsawon rayuwarsa, da Musulmi ya yi ta tu'amuli a qasar Kuwait, da qasar Sudan, kai har ma da Nijeriya ta Arewa. Saboda haka ya fahimci wannan Addini sosai don haka ne yake daraja xabi'u da halayen mabiya Addinin musulunci. Daga Sakkwato sai ya wuce garin Gwandu a rangadinsa na bankwana da Arewa.

Bankwana da Gawain Bell a Gwandu

Sir Gawain Bell, Gwamna mai ritaya ya ce: "Nijeriya ta Arewa ta yi sa'a matuqar gaske da ta samu nagartattun shugabanni da suke jagorantarta a kowane vangare na tasowarta zuwa ga samun 'yancin kai. Mai girma na amsa jawabin bankwana da Sarkin Gwandu, Alhaji Haruna da 'yan Majalisarsa suka yi masa a Fadarsa ne, a ran 3 ga Yunin shekarar 1962, a lokacin da ya kai ziyarar bankwana da su. A wannan lokaci ne ya isa Birnin Kebbi a kan hanyarsa ta ziyarar lardin Sakkwato. gwamnan ya ce da su ya ji daxin zamansa a Arewa, a duk inda kuma ya kai ziyara, jama'a na lale da marhaban da shi."

Sir Gawain Bell ya ce, abin alfahari ne da ya zo Nijeriya a dai-dai lokacin da wannan qasa za ta kai ga zama 'yantattar qasa mai mulkin kanta. Duk a wannan lokaci komai na tafiya cikin lumana da zaman lafiya. A kuma wannan lokaci ne shugabannin Arewa ke qoqari matuqa tare da nuna basira wajen ciyar da Arewa gaba don ta kamo jihohin Gabas da Yamma. Ya qara da cewa babu abin da yake jin daxin yi da ya fi yin rangadin larduna, wanda yin hakan yana bashi damar haxuwa da qabilu ir-iri, yana kuma qaruwa da hanyoyin rayuwarsu.

Daga qarshe gwamnan ya miqa godiyarsa ga Firimiya wanda ya taso takanas don ya taya shi wannan ziyara ta bankwana a lardin Sakkwato.

---

[1] *Ibid.*

A jawabin maraba da baqo da Sarkin Gwandu Alhaji Haruna ya yi, ya ce abin baqin ciki ne Mai girma zai tafi. Ya kuma yabawa kyawawan halayensa, ya kuma yi masa fatan zaman lafiya da jin daxi a lokacin wannan ritaya ta sa. Don qayatarwa da ziyarar sai Gwamna da Uwargidansa, da Firimiya, da Alhaji Ibrahim Biu suka je kallon Wasan Kamun Kifi.[1]

A lokacin da Gwamna mai ritaya ke rangadin bankwana da Arewa, ita Uwargidansa wani biki na musamman aka yi mata don a ce mata adabo, sai wata rana.

Sir Gawain Bell ya Bar Arewa

An yi wani xan qarammin biki mai qayatarwa wanda qungiyar *Red Cross Society* reshen Arewa ta yiwa shugaban wannan qungiya mai ritaya wato Uwargidan Gwamna Lady Bell. Wannan qungiya ta nuna abubuwanta masu yawa da ta yi a Nijeriya .

A jawabinsa, Shugaban Majalisar Wakilai, Alhaji Umaru Gwandu ya bayyana tarihin wannan qungiya da ci gaban da ta samu a Nijeriya. Shugaban ya kuma yi godiya ga Lady Bell, a inda ya ce ta hanyar tane masu muqami da yawa suka nuna sha'awarsu ga wannan qungiya da aikace-aikacenta. Daga nan sai Uwargidan Gwamna mai ritaya ta mayar da jawabi.[2]

A jawabinta ta samu nuna godiyarta ne ga waxanda suka xauki wahalhalun shirya wasanni masu qayatarwa, wanda ta ce sun ba ta sha'awa ainun. Duk da haka ta ce akwai abubuwa da yawa waxanda qungiyar za ta yi wajen taimakon marasa galihu a wannan jiha. Daga bisani an yiwa Lady Bell kyautar wata azurfa da aka qawata da taswirar Nijeriya, saboda nuna jin daxi da muhimman ayyukan da ta yi.

A cikin xaruruwan mutanen da suka halarci wannan biki harda Gwamna mai ritaya, Sir Gawain Bell, da shugaban riqo na N.R.D.C, Alhaji Muhammadu Ladan, xan Iyan Zazzau, da Kwamishinan riqo, na 'yan Sanda Alhaji Kam Salem, da sauran manyan qusoshin gwamnati.

Ranar Litinin, 18 ga Yunin shekarar 1962, aka yi qasaitaccen taro na Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai gaba xaya a subuwar Majalisa saboda yi wa gwamnan Arewa, Sir Gawain Bell, shi da uwargidasa, ban kwana. A jawabin da Firimiya ya yi, jawabin da ya sha tafi a Majalisa, ya bayyana irin kyawawan ayyukan da Sir Gawain Bell ya yi wa qasar nan, ayyukan da ba za a mance da su ba har abada. Daga cikin manyan da suka halarci kallon taron ban kwana xin nan, har da Razdantai da yawa, Baqar Fata da turawa, manya-manyan ma'aikatan gwamnati da na En'e-En'e da dai sauran manyan mutane daga wurare dabam daban.

---

[1] NC, Asabar, 9/6/1962, shafi na 12

[2] NC, No 1044, Asabar 16/6/1962, shafi na 1

Lokacin da Gwamna ya isa qofar Majalisa, cikin farin ciki da fara'a, kafin ya shiga Majalisa, sai da ya karvi gaisuwa kuma ya kewaya faretin da 'yan Sanda suka yi a bakin Majalisa. Daga nan ne Akawun Majalisa shi da Shugaban Majalisar Wakilai da na Sarakuna tare da Firimiya suka yi wa Gwamna jagora zuwa cikin Majalisa inda Firimiya ya.

Mutane da yawa sun hallara a tashar jirgi na Kaduna Jamsin, a wani qasaitaccen biki da aka yi na bankwana da Gwamna ma ritaya da Uwargidarsa Lady Bell. Bayan wannan biki ne, wani jirgi na musamman zai xauke su daga Kaduna zuwa Ikko, a matakin farko akan hanyar zuwa Ingila, bayan Gwamna ya yi ritaya a ran Talata da Yamma.

Gwamna mai ritaya, na isowa Kaduna Jamsin sai ya tarar da dafifin jama'a da suka haxa da 'yan 'Boys' Scouts', da 'yan Girls' Guides' da jami'an kula da lafiyana qungiyar *Red Cross Society*. Waxannan jama'a na murna da ganinsa, sai ya wucewajen duba faretin ban girma da sojan Bataliya ta uku, wato *third Battalion* ta yi masa. Daga nan sai Sir Gawain Bell da Uwargidarsa tare da Firimiya da sabon Gwamna Sir Kashim suka yi masa rakiya inda manyan mutane da xaruruwan jama'a daga dukkan sassan Arewa suka yi masa adabo, sai wata rana.[1]

A cikin waxannan manyan mutane, harda, Alhaji Sir Sarkin Musulmi Abubakar na Uku, da Sarkin Kano, Alhaji Sir Muhammadu Sunusi, da Sarkin Gwandu, Alhaji Haruna, da Sarkin Katsina, Alhaji Sir Usman Nagogo, da Sarkin Ilori, Malam Sulu Gambari, da Attah na Igala, Malam Aliyu Obaje. Haka kuma wannan taro ya haxa da Ministoci, da Falimantare Sakatarori, da Cifjojin Arewa Mai girma Mai shari'a Hurley, da Alqalin alqalai Mai girma Alhaji Abubakar Gumi da sauran manyan qusoshin gwamnati.[2]

A dai-dai lokacin da targunan jirgin da ya xauki Sir Gawain Bell da ayarinsa, sai da 'yan budujala suka rera taken bankwana da Hausa, sa'an nan aka yi harbi sau goma sha-bakwai na gaisuwa. A cikin 'yan rakiyar sa a cikin wannan jirgi zuwa Ikko, harda Ministan Harkokin cikin Gida, Alhaji Muhammadu Kabir, Ciroman Katagun, da Falimantare Sakatare na Ma'aikatar jin Xaxi da haxa kan jama'a, Mr. Edmond Mamiso.[3]

Maraba da Sir Kashim

Alhamdu Lillahi, ranar da aka qosa ta zo, ga shi ta zo, har ma ta wuce, yanzu ta bar mu muna ta Murna da farin ciki. Duk jama'ar Arewa, ba ranar da suka qosa ta zo kamar ranar Alhamis, 21 ga Yunin shekarar 1962. Mene ne ya sa aka qosa ta

---

1 NC, No 1044, Asabar, 16/6/1962, shafi na 1

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*

zo, domin ita ce aka ajiye ranar rantsar da sabon gwamnanmu na Nijeriya ta Arewa, gwamnan da yake shi ne xan Arewa na farko da ya fara hawa irin wannan muqami. To, cikin ikon Ubangiji, bisa rahamarSa, ga shi ranar ta zo kuma an rantsar da Sir Kashim Ibrahim don zama gwamnan Arewa kamar yadda aka ajiye. Yanzu Sir Kashim dai ya haye gadon sarautar gwamnan Arewa, Allah Ya riqam masa.

Irin qasaitaccen taron da aka yi don bikin rantsar da Sir Kashim, ba shakka ya zama abin alfahari, domin kuwa takanas Mai girma Shehun Barno mai shekaru fiye da casa'in ya halarci wurin bikin rantsuwar. Kun san dai Shehun Barno ya daxen gaske rabonsa da zuwa Kaduna saboda manyanta, to, duk da wannan lalura tasa, don nuna godiya da farin ciki ga gwamnati, takanas ta jirgin sama shi da kansa ya taso zuwa Kaduna wurin bikin rantsuwar.

Da qarfe huxu na Yamma a jiya xin nan ne gwamnan Nijeriya ta Arewa na da, Sir Gawain Bell, shi da uwargidansa, suka bar Ikko ta jirgin ruwa zuwa London don hutawa. Ya yi ban kwana da Nijeriya bisa nuna jin daxi. A lokacin ne aka rantsar da Sir Kashim Ibrahim.

Irin shagulgulan da aka fara yi a wannan rana don bikin murnar rantsar da Gwamna Sir Kashim Ibrahim, suna da yawa. A wannan ranar tarihi xin nan ma, irin shagalin da za a sake yi a Kaduna, da maraice, abin ba dama. Saboda irin ximbin mutanen da ke maqare da Kaduna don bikin da kuma irin wasannin da za a yi ta yi. Hasali ma dai daga ranar, Asabar, lardunan Nijeriya ta Arewa za su ci gaba da wasanni iri-iri na nuna farin ciki da murna, za a kuwa yi kwanaki ana wasannin.

Kamar yadda aka saba, Cifjojin Jihar Arewa ne ya rantsar da sabon Gwamna Sir Kashim Ibrahim, sa'an nan su biyu suka sa hannu a littafin rantsuwa. Mai martaba Firimiyan Arewa ya yi daddaxan jawabi, a ciki ya yabi Sir Kashim kuma ya jawo hankalinsa bisa babban nauyin da ya hau kansa. Shi ma Sir Kashim ya yi kyakkyawar magana.

Irin shagulgulan da za a yi a yau xin nan Jumma'a, 22 ga Yuni, 1962, su ne za a yi wata qasaitacciyar liyafa da qarfe 4 da rabi na maraicce a gidan Gwamna. Za a kuma yi wasan qwallo a filin wasa na Kaduna tsakanin 'yan wasan Kaduna da na Zariya don murna. Da qarfe bakwai da rabi na Yamma, za a yi raye-raye da kaxe-kaxen al'ada.

A ranar Asabar, 23 ga Yuni, da qarfe bakwai da rabi na Yamma, za a yi wasan rawar Tattoo a filin sukuwa. Shahararrun masu kixan badujala na Soja da 'yan Sanda, waxanda suka zo takanas daga Ikko, su ne za su yi kaxe-kaxe wasan. Malam, gobe kam ba dama, kai ma kada ka bari wannan kallo ya wuce maka ko da yake za a yi a garinku ko qauycenku. Duka dai muna wannan shagali don murnar naxa namu ne ya zama gwamnanmu na Arewa. Allah Ya riqam masa kuma ya ba shi ikon tafiyar da sha'anin mulkinmu bisa adalci. Amin.

A ranar Alhamis 21, ga watan Yuni Babban mai shari'a na Arewacin Nijeriya mai shari'a Hurtey ya rantsar da Gwamna xan qasa na farko, Mai girma Sir Kashim Ibrahim K.C.M.G, C.B.E, a bikin rantsarwar da ya gudana a sabon xakin Majalisar Dokoki da ke Kaduna. Ya gaji Sir Gawain Bell da ya yi ritaya a kwanan nan.

Firimiya ya yi jawabin marhabin, inda sabon gwamnan ya mayar da jawabi. Mutane masu yawan gaske suka shaida wannan biki ciki har da Firayim Ministan qasar nan Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa, da Firimiyan Jihar Gabas, Dr. M. I. Okpara, da babban mai shari'a na Tarayyar qasar nan, Sir Adetokumbo Ademola, da gwamnan Gabashin Nijeriya, Sir, Francis Ibiam.

A lokacin da Mai girma ya isa Majalisar ya sadu da Firimiya: inda suka shiga zuwa cikin Majalisar a gaban jerin gwanon baqi. Daga nan sai babban mai shari'a na Arewa ya rantsar da shi, shi kuma babban Alqalin Alqalai wato Grand Khadi Alhaji Abubakar Gumi ya fassara zuwa Hausa. Firimiya ne ya fara gabatar da jawabinsa.

Jawabin Firimiya

Mai girma,

Ina somawa da sunan Ubangiji, Mai Rahama, Mai Jinkai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu. Wannan muhimmiyar rana ce a tarihin wannan shahararren yanki namu, kuma wannan dama ce ta mu yi addu'ar neman tsira da kuma jagora daga Ubangiji.

Ba a daxe da rantsar da kai ba a matsayin gwamnan Jihar Arewa. Muna farin cikin Ubangiji Ya bar mu a raye domin mu shaida wannan muhimmiyar rana a tarihin rayuwar qasarmu.

Saboda haka muna godiya ga Ubangiji da AnnabinSa Muhammad, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

A biki irin wannan, akan tavo tarihin mutumin da kuma aikin da ya yi wa al'umma. Mai girma na sanka kuma mu abokai ne tun muna 'yan yara. Mun soma gamuwa a babbar makarantar nan ta Kwalejin Katsina. Ina iya tunawa da wannan lokaci muna yara, lokacin yaranta kuma babu abin da ya sha mana kai. Ina xaukar kaina da sauran waxanda suka yi karatu a Kwalejin Katsina a matsayin waxanda suka yi sa'ar shiga wannan fitacciyar makarantar wacce ta yi wa Arewa aiki da kuma qasa baki xaya.

A wancan lokaci ba mu samu abubuwan da sauki ba; babu wasu abubuwa na jin daxi kamar yadda matasan yanzu suka fi fifitawa a yau.

Musamman zan iya tunawa da doguwar tafiyar da muka saba yi daga garuruwarmu daban-daban zuwa Katsina, da kuma sake

komawa gida idan an yi hutu. Kai daga Barno, ni kuma daga Sakkwato. A cikinmu akwai waxanda suke zuwa daga nisar duniya kuma da qafa suke zuwa saboda a wancan lokaci babu hanyoyi, babu motoci. Waxanda ke da gata a cikinmu su ne ke zuwa akan dawakai. Ina jin gaskiya ne idan na ce mu da muke a Kwalejin Katsina mun girma tare da qasar nan kuma mun shaida matakai daban-daban na ci gabanta da kuma bunqasarta. Yawancinmu a matsayinmu na shugabannin qasar nan a yanzu, mun fuskacin gaba.

Yanzun zan juya ga aikin da Mai girma ka yi wa Barno; da Arewa da kuma qasa baki xaya. Kai kamar yawancinmu nan yawancin rayuwarka ta matashi ka yi ta ne a matsayin Malamin Makaranta, kana baiwa 'yan'uwanka maza ilimin yiwa jama'armu aiki. Daga bisani ka zama xan Majalisar Wakilai tare da aiki tuquru a matsayin Minista a matakin tarayya da na yanki. Ayyukan da ka yi wa qasar nan a lokacin kana Minista ba za a tava mantawa da shi ba. Sannan aka buqaceka a En'e ta Barno nan ma ka baiwa maraxa kunya ka yi aiki tuquru ga En'e da jama'ar masarautar. Aikin da ka yi a wannan waje ba za a tava mancewa da shi ba a tarihin wannan mashahuriyar Masarauta. Tashinka daga Barno zai zama babban rashi.

Sai dai dole abin da zai qarfafa maka gwiwa shi ne kiranka aka yi ka yiwa al'umma Mai girma ta Arewacin Nijeriya aiki. Gudunmawar daka bayar domin ci gaban Barno ba qarama ba ce kuma na tabbata mutane suna matuqar godiya gareka. Sai dai a wannan lokaci ayyukan na Barno ba su tsaya ga jama'ar Lardinka kaxai ba; kai dattijo ne da ya yi aiki a Majalisarmu. Kuma ka tava yin shugabancin Kwalejin Kimiyya da Fasaha, wacce cibiya ce da ke da muhimmancin gaske wajen horar da matasanmu maza da mata akan gudunmawar da za su ba da ga wannan yanki na mu mai faxi da kuma qasa baki xaya.

Ko a baya-bayan nan ma a matsayinka na shugaban Majalisar Riqon Kwarya ta sabuwar Jami'armu, ka dage wajen kafa qwaqqwaran ginshiqi na ci gaban cibiyar.

Yadda kowa ya yi gagarumar na'am ciki da wajen qasar nan da ya ji sanarwar naxinka, ko shakka babu ta tabbatar mini da cewa ba a yi zaven tumun dare ba. Na samu xinbin wasiqu da saqo na tangaraho da ke nuni da hakan kuma ina yi maka addu'ar Allah Ya taya ka riqo a wannan sabon muqami naka.

Mai girma har zuwa yau xin nan kai Kanuri ne daga Barno. A yanzu a matsayinka na gwamnanmu na wannan gagarumin yanki namu, kai Gwamna ne na Arewacin Nijeriya Ko da yake ka yi

tafiye-tafiye, ka leqa dukkan faxin qasar nan, har yanzu akwai inda baka leqa ba. Kamar dukkanmu nan, zaka samu cewa akwai mutanenmu da dama da baka tava saduwa da su ba da rayuwarsu take iya zama baquwa gareka. A nan zan ba ka shawarwari ya kamata ka zagaya Arewa domin sani da kuma saduwa da qarin wasu mutanen namu, su ma kuma su sanka. Ina maka addu'ar Allah Ya baka iko da qarfin gwiwar gudanar da wannan muhimmin vangare na sabbin ayyukan da suka hau kanka.

Ni a rawa vangaren a yanzu zan yi amfani da wannan dama in qara duqufa ga yi wa Arewacin Nijeriya da Nijeriya baki xaya aiki. In muka haxa qarfi wuri guda, ko shakka babu za mu yi aiki domin amfanar jama'armu da ba da kyakkyawan misali ga kowa da kowa ya bi a wannan gagarumin aiki na gina qwaqqwarar qasa ta Arewa mai haxin kai da yalwa. Na yi cikakken imanin cewa alqiblar wannan gagarumar qasar tamu mai kyau ce tare da roqon Allah Ya yi mana jagora dukkanmu ga gudanar da waxannan ayyuka namu.

Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Sardaunan Sakkwato yana gama jawabinsa mai ma'ana da farantawa, sai sabon gwamnan Jihar Arewa Alhaji Sir Kashim Ibrahim ya miqe don ya mayar da jawabi.

Jawabin Sabon Gwamna

Mai girma Firimiya:

Da Sunan Allah Mai girma da Rahama, tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu.

Na miqe ne a yanzu, Mr. Firimiya domin yi maka matuqar godiya a game da kyawawan kalamai da ka yi a game da ni.

Gaskiya na yi matuqar jin daxin, da martabawa a game da abin da ka faxi, da musamman tavo lokacin da muke Kwaleji. Kamar yadda ka faxi a wancan lokaci da muke Kwalejin Katsina muna cikin mawuyacin hali, amma na tabbata za ka yarda da ni cewa cikin rahamar Ubangiji mun amfana da wancan horo, da shi ya sa muka fi dacewa da kuma zama a shirye domin cike muhimman gurabe na shugabanci da aka kira mu mu riqe.

Mr. Firimiya ka kuma ambato ayyukan da na yi a Barno. A nan zan iya cewa na yi abin da ya kamata in yi ne a matsayin wanda jama'arsa ta kira shi a wani mawuyacin lokaci domin taimaka masu warware matsalolinsu. Idan an yaba da wannan xan aiki da na yi ba

a Barno kawai ba, har ma a yankin Arewa baki xaya, to zan iya cewa na gode.

Har ila yau ka ce barina Barno za ta zama babbar rashi ga jama'ar Barno zan iya baka tabbacin cewa mutanen Barno mutane ne da ke da matuqar qaunar ci gaban Arewa kuma na tabbata ba su yi nadamar barinsu da na yi don zuwa yi wa Arewa aiki ba.

Har ila yau ka ce duk da yake ina aiki ne a Barno amma aikin bai tsaya ga Lardin Barno kawai ba; zan baiwa Mr. Firimiya tabbacin cewa a kowanne lokaci ina sha'awar yin aiki ba a Barno kawai ba, har ma ga Arewa da kuma qasa baki xaya idan aka bani dama. Na kuma yarda da kai da ka ce daga yau ni ba Kanuri ba ne daga Barno, illa xan Arewa. Zan baka tabbacin cewa daga yau ni ba Kanuri bane, xan Arewacin Nijeriya ne. Har ila yau zan baka tabbacin cewa tun lokaci da aka vullo da batun kishin Arewa, na sanyawa kaina tunanin ni xan Arewa ne mai kishinta ba Kanuri ba.

Na yi aiki kamar yadda ka ce a matsayin Minista a tsakiya da kuma a nan yankin Arewa, kuma ina so in yi bayani a nan cewa na ji daxin waxancan lokuta fiye da yadda ake zatto kuma ilimin da na samu a waxannan ayyuka sun zama babban jari gareni. Ina farin cikin cewa a qarqashin iya shugabancinka, yankin nan ya samu ci gaba ba qarami ba, sannan uwa uba cikin cikakkiyar zaman lafiya da walwala.

A duk faxin Arewa babu wanda ya yi qoqarin da ka yi na haxa kan mutanen Arewa da ke da alqibla daban-daban zuwa zama tsintsiya xaya madaurinki guda cikin walwala. Saboda haka na yi aminnar cewa ni da kai da sauran jama'armu za mu haxu mu yi iya qoqarinmu domin ci gaba da raya Haxaxxiyar Arewa mai yelwa da bunqasa da kwanciyar hankali. Dole ne mu duba gaba a kowanne lokaci tare da tabbatar da mun xore da ci gaba. Babu sanya, babu sako-sako a wannan qoqari na ku; a maimakon haka ya kamata mu qara himma da azama da xagewa domin qara kyautata kowanne vangare na kyautata jin daxin jama'armu.

Na yi matuqar farin cikin da yadda jama'armu ta yi na'am da labarin naxani a matsayin gwamnan wannan yanki. Zan ba su tabbaci su dukkansu cewa zan yi iya qoqarina don tabbatar da ba a ci amanarsu da aka xauka mana ba.

Ina mai godiya gareka da kuma dukkan mutanen Arewa da suka taru a nan a yau domin shaida wannan biki zan yi qoqarina a wannan aiki da ke gabana.

Saboda haka nake cewa in Allah Ya yarda daga wannan rana zan sadaukar da dukkan lokacina, da dukkan ni kaina, da dukkan fatata, da tafiyar da dukkan rayuwata ga bautawa wannan yanki. Allah Ya yi mana jagora bisa tafarkin da ya dace, Amin.[1]

Sabon Gwamna na barin Majalisar sai aka soma yi masa gaisuwa ta ban girma da sara masa, daga nan Runduna ta farko ta Recce ta harba bindiga guda goma sha-bakwai domin girmama shi. Daga nan ya duba faretin ban girma, sai jerin gwanon qananan motoci a titin King George zuwa titin Prince Edward ya biyo ta cikin taron jama'a da ke ta shewa suna jinjina masa.

Arewa Jiha ce mai ximbin tarihi wadda take tagomashin Jiha, a Nijeriya. Shugabannin Arewa sun kai ta ga shahara, saboda haka ne ta qara yin fice da suna a duniya. Abin da ake buqata a wancan zamani shi ne Mai martaba Sarauniya ta zo Arewa ta ga Jiha mai bambanci da banmamaki.

Nijeriya na Buqatar Ganin Sarauniya

Nijeriya ta Arewa ce kan gaba wajen bayyana ra'ayinta na buqatar zuwan Mai martaba Sarauniya wannan qasa. Tun daga watan Disamban shekarar 1952 jama'a ke faxin ra'ayoyinsu da bayar da dalilan cancantar ziyarar Sarauniya ga wannan qasa. A kan wannan batu ne ma aka bada waxannan dalilai musamman a lokacin da Gwamna Janar ya ga wannan lokaci ya zo:

...qasar Nijeriya a yau, ita ce qasa mafi girma cikin qasashen da ke qarqashin mulkin Sarauniya, (Colonial Territories), lallai ya kamata mu roqa Sarauniya ta yi qoqari wata rana ta ziyarce mu. A lokacin da yake Indiya ce babba cikin qasashen nan, Sarakunan Ingila da 'ya 'yansu sun ziyarce ta. Mun tabbata zuwan Sarauniya Nijeriya yana daga cikin manyan buqatun Nijeriya.

Editan Gaskiya sai ya ce: "To, Fa. Ga abin da muka faxa cikin shekarar 1952, ya fito daga bakin Mai girma cikin shekarar 1954. Ga abin da muka faxa cikin Disamban shekarar 1952, Wakilan Majalisar Nijeriya da waxanda suka yi shiru, domin sun yarda da abubuwan da wakilan da suka yi magana suka ce, sun yarda "zuwan Sarauniya Nijeriya yana daga cikin manyan buqatun mutanen Nijeriya."[2]

A zaman da Wakilan Nijeriya suka yi, gwamnan Nijeriya bai yi qwauron baki ba, da ya fito ya faxi ra'ayinsa cewa: "Wata qila ba za ace mun yi shisshigi ba, im

---

[1] NC, No. 1,0407 Laraba, 27/6/1962, shafi na 1

[2] GTK 17/3/1953: Sharhin Edita.

muka ce, muna fata wata rana Sarauniya za ta sami lokaci, ko da yake tana da ximbin sauran ayyuka, ta ziyarci mutanenta a Nijeriya."[1]

Idan ba a manta ba, a farkon zuwan Sir John Mcpherson wannan qasa, a matsayinsa na Gwamna Janar, Sakkwato ce ta yi masa lale da marhabin da wata qwarqwar yar Hawan Bangirma wadda ta qayatar da shi matuqar gaske. Tun daga wannan lokaci ne yake zakwaxin ganin Mai martaba Sarauniya ta samu ganin qasaitacciyar Daba a Arewa. Domin cika wannan buri nasa ne sai a cikin jawabinsa na buxe taron Majalisar Nijeriya, a zamanta na duba Istimat na quxin da gwamnatin Nijeriya za ta kashe kan ayyukan qasa, a shekarar Kuxi ta shekarar 1953 zuwa 1954 ya gabatarda wannan buqata.

Haka kuma Alhaji Shehu Ahmadu, Madakin Kano, a cikin jawabin da ya yi a Majalisar Wakilai ya ce: "Muna son Mai girma Sarauniyar Ingila ta ziyarce mu, domin shekara 23 ke nan, tun lokacin da *Prince of Wales* ya kawo ziyara a wannan qasa.[2]" Kwaram! Sai ga Nijeriya na shirye-shiryen karvar bakuncin Mai martaba Sarauniya a farkon shekarar 1956.

---

1 *Ibid*

2 *GTK* 17/3/1954, shafi na 12

KASHI NA GOMA SHA-BIYAR

Ziyarar Sarauniyar Ingila

A qarshen watan Janairu, 1956 aka ba da sanarwar cewa Sarauniyar Ingila da mijinta za su kawo ziyara a Nijeriya. A dalilin haka sai idon duniya duk ya juyo ga Nijeriya. Domin kuwa Sarauniya ba ta tava ziyartar wata qasa a Afirka ba, sai Nijeriya. A dalilin haka sai aka shirya za ta ziyarci Kaduna da Jos, da Enugu da Birnin Kano. Garin Kaduna ne zai karvi wannan baquwa mai daraja saboda haka sai aka yi masa gyare-gyaren da za su qawatashi. Cikin watan Janairu 1956 irin shirye-shiryen da a ke ta yi saboda ziyarar da Sarauniya za ta yi, sun kai inda suka kai. An yi amfani da da hikima wajen yin ayyuka ma su qawatarwa sosai.

Jama'ar Nijeriya ta Arewa duka suna farin cikin isowar Sarauniyar Ingila Elizabeth ta Biyu, da Mijinta Duke of Edinburgh, domin su ga jama'a jama'a su gan su. Ita Sarauniya Elizabeth an haife ta ran 21 ga Afril, 1926. A watan Afril na shekarar 1956, ta cika shekara ke nan a duniya.

Wani mai ba da labarinta ya ce Allah mai iko! Lokacin da aka haife ta ban da Allah, babu wanda ya san za ta zama Sarauniyarmu. Domin lokacin, zamanin kakanta marigayi Sarki George na Biyar, babban kawunta a lokacin sarautarsa ita ce Prince of Wales, yanzu kuwa Duke of Windsor, shi ne mai jiran gado. A sa'an nan yana tsakiyar koyon irin yadda ya gaji tsohonsa, zai riqe gadon nan mulkin nan na Ingila.

In an dubi wannan lokacin da tsarin sarauta a Ingila ba za a tsammaci tsohon Sarauniya zai sami hawa gadon sarautar. Ingila ba ma, balle ita. Amma Ubangiji ya yi ta Sarauniya sai kawunta, yana Sarki Edward na Takwas ya yi marabus. Tsohonta ya zama Sarki George na shida. Yana rasuwa, ta hau gadon kakanninta.

A 'yar qaramar Majami'an nan ta Buckingham Palace aka raxa mata suna Elizabeth Alexandra Mary. Alexandra, xin nan, sunan kakarkakarta ne, Sararuniya Alexandra, Mary kuwa sunan kakarta ta wajen uba-dukansu Sarauniyoyin Ingila ne. Yawancin quruciya tata a gidan tsohonta na London, 145 Piccadilly, ta yi ta. Wani lokaci kuwa ta kan je ta yi 'yan kwanaki wurin kakanninta George na Biyar da Sarauniya Mary, ko kuwa awurin kakanninta a wajen uwa, Eadda Countess of Strathmore, iyayen gyatumarta, ana kiran gidan Glamis Castle, a Scotland. Ita da qanwarta Margaret, sun sami ilmi a gida ne, ba a wata makaranta ba.[1]

---

[1] GTK 1/2/1956.

Cikin Janairu, 1936, kakanta Sarki George na Biyar ya rasu, a lokacin ta cika shekara goma a duniya. Kawunta Prince of Wales ya hau gado, bai shekara ba ya yi murabus, tsohonta ya gaje shi. Hawan tsohonta gado, sai ta zama mai jiran gadon sarautar Ingila, don kawunta ya ce "da shi da dukkan 'ya'yan da zai haifa a gaba ma, ba su bukatar sarautar Ingila". Elizabeth sai ta shiga karance-karancen yadda a ke tafiyad da mulki". Sir Henry Marten ne malaminta. Ta duqufa sosai wajen qara wa kanta ilmi.

Tana qara girma, ana qara cusa ta cikin ayyukan mulki, don ta saba, kafin nauyinsa, duka ya hau kanta, yadda ya hau a yanzu. Tana da shekara goma sha huxu ta fara yi wa yaran duniya jawabi a rediyon Ingila,wato cikin Oktoba, 1940. Tun a wannan lokacin wani mai hangen nesa ya ce, "Muryan nan ta dace da muryar wadda za ta zama Sarauniya wata rana. Idan a gaba ba za a daina naxa sarauniyoyi a Ingila ba, yarinyan nan za ta zama Sarauniya."[1]

Cikin 1942, tana da shekara goma sha shida, tsohonta ya naxa takanar ta 'yan Gadin Fada wato, "Grenadier Guards". Tun daga lokacin nan ta fara fitowa fili tana rungumar ayyukan mulki. Ta fara raka iyayenta tafiya-tafiyen da suka yi ta yi. A zamanin yaqi, lokacin da tsohonta ya ziyarci fagen yaqin Italiya, tana cikin waxanda aka naxa, Council of State, domin su riqe masa mulki, kafin ya komo.

Ko da ya ke ba a cika ganinta ba sai da hujja, amma ita da qawayenta su kan yi ta wasanni iri-iri a fada, da sauran wurare. Tana son sana'a da waqe-waqe da kaxe-kaxe. Su rawa duk takan yi da qawayenta a Windsor.Ta gwanance a hawan doki, ta iya ninqaya a ruwa. Har ta ci garkuwa, don kuvutad da wani daga halaka. Tana da shekara goma sha xaya ta zama Girl Guide, ta kuma zama Scout a teku. Ta shiga aikin sojan mata. Ta yi kos na tuqin mota, ta sami lasin. Bayan yaqi, cikin 1949, sa'ad da aka shirya aikin soja mata sosai, ta zama Honorary Senior Controller.

Bayan yaqi, sai ayyuka suka yi ta vumvunto mata. Ta zama shugaba cikin jam'iyyoyin kyautata zaman jama'a iri-iri. Ta yi ta tafiye-tafiye zuwa wurare da yawa a Ingila. Tana rangadi ta cika shekara ishirin da xaya na haihuwa tare da iyayenta. Daga Capetown a Afirka ta Kudu, ranar da ta kai ishirin da xaya, ta yi gaba gare ku, jama'ar duniya, rayuwata ko tana da tsawo, ko kuwa gajeriya ce, zan qare ta cikin yi muku aiki, ku da dangina. Amma wace ni, da zan sami qarfin yin ximbin ayyukan nan, im ba da taimakonku ba. Ina kuwa roqonku ku yi mini taimako. Na tabbata za ku taimake ni, ba da wani qusuri ba. Ta ce "Allah ya rufe ni da cika wannan rantsuwa da alqawari nawa."[2] duniya har yau tana tunawa da jawabin nan.

---

[1] GTK 1/2/1956.

[2] *Ibid.*

Ita da iyayenta ba su jima da dawowa daga rangadin nan ba, tsohonta ya ce ya ba da ita aure ga Leftana Philip Mountbatten. Ran 20 ga Nuwamba, 1947 aka yi bikin. Cikin 1948 ta haifi mai jiran gado na yanzu, Prince Charles, sarautarsa a wancan lokaci ita ce Duke of Cornwall. Cikin 1950 ta haifi qanwarsa, Princess Anne.

A wannan zamani nata, Sarauniya ta yi tafiye-tafiye masu yawa. Tare da Mijinta, sun je Faransi, Greece, Italiya da Norway. Ta kuma ziyarci qasashe da dama waxanda ke zaman abota da Ingila. Daga 1953 zuwa 1954, ta ziyarci Bermuda, Jamaica, Fiji, Tonga, New Zealand, Australia, Ceylon, Malta da Gibralter. Da ma dai ita da Mijinta sun je Canada.

A ranar Laraba 6 ga Fabrairu, 1952, da dare Majalisar masu zaven Sarki, Council of Accession, ta yi taronta a fadar da ke kira St. Jame's Palace. A nan suka tabbatar, Gimibiya Elizabeth ta gaji tsohonta, ta zama Sarauniya Elizabeth ta Biyu.

Ran 7 ga wata, ta iso London da Yamma a cikin jirgin sama, a nan filin ta sadu da tsohuwa tata Elizabeth, da kawunta Duke of Gloucester, da Waziri Churchill, su Attice, da sauran shugabannin Ingila.

"Mafi muhimmancin sha'ani game da wannan babbar baquwa ta Jihar Arewa, shi ne sanya mata kambinta na sarautar Ingila da mulkin Ingila. An sa mata shi ran 2 ga Yuni, 1953.[1]

An yi qasai taccen biki a wannan inda aka gayyato manyan mutane daga Turai da qasashen da ke qawance da Ingila wato Commonwealth Nations. Waxanda suka wakilci Arewa a ranar bikin naxin Sarauniyar su ne: Shettima Kashim, Ministan Tarayya na ji daxin jama'a, da Mr. Peter Achimugu, Ministan Masan'antu na Jihar Arewa da Malam Nagwamatse, tsohon hedmasta, kuma mashahurin malamin Makaranta. M. Isa Kaita Sakataren En'e ta Katsina kuma xan Majalisar Wakilai, ya tafi a Wakilin reshen Nijeriya na qungiyar masu bin mulkin Falimantare na qasashe masu qawance da Ingila.[2]

Idan muka dubi labarin mijinta sai muga shi ya fi dacewa da ita don shi ma gwarzo ne. A nan za mu ba dea taqaitaccen tarihin mijin Sarauniya Elizabeth ne, wato Duke of Edinburgh, wanda ya rako Sarauniya Nijeriya. Shi kuwa tun sa'ad da ya ke makaranta a Moray, Firth; ya saba da ruwan teku. Ya yi ayyuka masu wuya a jiragen ruwan Ingila, har ya kai ga shugabantar jirgin ruwan da ya ke aiki a cikinsa. Bai so ba da ya bar aikin jiragen ruwa saboda ayyukan sarauta. Amma duk da haka muddin yana iya komawa ayyukan jiragen ruwa zai koma ne.

---

1 GTK 1/2/1956.

2 NC, 28/5/1953, shafi na 1

Yana da shekara goma sha takwas ya shiga aikin jiragen ruwan yaqi na Ingila yana "Cadet" wato kurtu, aka aika da shi koleji ta jiragen ruwan Sarki a Dart mouth. A can ya sami lambar Sarki wadda a ke kira King's Dirk, saboda nuna qwazo, ba kamarsa duk a makarantar game da kowane aiki. Ya sake samun kyauta, don ya yi wa duk 'yan ajinsu fas.[1]

Cikin watan Janairu, 1940 ya shiga teku a jirgin da a ke kira Ramillies. A wannan shekara ne ya fara gano qasar New Zealand. Bayan ya shekara teku aka mai da shi aiki a cikin jirgin ruwan yaqi na sosai. A wannan karo neya nuna bajintar da ta ba shi lambar yaqi babba ta qasarsu, Greece.

Daga can kuma sai aka haxo shi da waxansu hafsoshi, su taho koyan aiki. Ya yi lambawan a fannoni dabam dabam sau huxu, ya yi lambatu sau guda.Cikin 1942 aka naxa shi mataimakin akin leftanan na jirgin yaqin da a ke kira Wallace. Yana da shekara ishirin da xaya da haihuwa yaci girma ya zama leftanan na farko.

A lokacin da jirgin su Phillip ya nufi Gabas ta Nesa, zai ratsa Suez Canal, jirgin magauta ya tasam masa. A nan ne ya gamu da tsaurin da bai tava gamuwa da irinsa ba. Amma take ya banke su, ya shige, ya tafi Japan. Can ya yi aiki a jirgin ruwan da a ke kira Destroyer Whelp. Can ya yi aiki har sai da Japan ta tuba, sa'an nan ya koma Ingila. Bayan ya yi aiki wata biyu, ya fita soja, amma bai bar jiragen ruwa ba.

Da fitarsa soja sai ya koma makaranta.Idan aka tashi daga makaranta, ya kan shiga tsakanin abokan aiki, ya yi raye-raye tare da su a kulob, ko ya shiga wasannin kurket lokacin da yake Corshan, nan ya shiga hidimar aure da Sarauniya Elizabeth (lokacin tana gimbiya). Yana tare da abokansa masu aikin jiragen ruwa, har zuwa darensa na qarshen gwaurantaka. Bayan ya yi aure ya zama Duke of Edinburgh.

A wani jawabi da ya tava yi a Edinburgh, mutum kusan dubu biyu sun saurare shi. Bayan minti 45 da ya yi yana magana duk xakin da aka taru sai da ya yi kamar zai tsage, saboda gunjin jama'a. Jawabinsa ya qayatad da su ainun. Daga nan ne ya fara nuna wa jama'ar wurin alamomin dacewa da auren Sarauniya ga mutumin da ya ratso muqami iri iri, musamman don qwazonsa da qoqarinsa.[2] Da faxin zuwan waxannan manyan baqi sai Nijeriya ta Arewa ta shiga qasaitaccen shirin karvarsu cikin daraja da karramawa.

---

[1] GTK 1/2/1956.

[2] *Ibid.*

Qasaitaccen Shiri

gwamnatin Arewa ta ware fam dubu xari (£100,000) domin kashewa akan shirin wannan ziyara. Amma duk da haka waxannan kuxi ba su isa ba. Saboda haka sai aka qara £100,000 don a cimma wannan shirin taron, da kuma qawata garuruwan da Sarauniya za ta ziyarta a Arewa, wato Kaduna, da Jos, da Makurxi da Birnin Kano. An kashe fam dubu maitan wajen wannan ziyara dake da muhimmanci qwarai da gaske.[1]

gwamnatin tsakiya ta ware fam dubu xari uku (£300,000) don qawata Ikko. gwamnatin Jihar Gabas da ta Yamma, kowacce ta ware £100,000 domin wannan ziyara a Jiharta. Saboda mu muna murnarmu ga wannan ziyara duk abin da aka kashe, in dai ba a sa mubazzaranci ba, bai yi yawa ba. Kuma ba ta'adin kuxi ba ne.[2]

Kuxin da aka ware don kashewa a Arewa saboda zuwan Mai martaba Sarauniyar Ingila, ba za'a iya qididdige daidai adadin abin da za a kashe a kan kowane abu ba. Don haka a kintace an ware fam dubu saba'in (£70,000) don kawo baqin da aka gayyata zuwa Kaduna, da dawakai da yam makaranta da 'yan sanda, malaman tsabta da dai sauransu. Wurin sauka da abincin baqin da na dawakai, zai ci fam xubu arba'in (£40,000). Don shirya babban filin da za a yi babban hawa don Sarauniya da kuma kewaye wuraren da za ta bi, za a kashe fam dubu goma sha biyar(£15,000). Gyaran hanyoyi da na waxansu gine-gine zai ci fam dubu ishirin(£20,000). Yin waxansu gine-gine don taryar Sarauniya a filayen jiragen sama na Kano,da Kaduna,da Jos da Makurxi, zai ci fam dubu takwas (£8,000). Waxannan na cikin ayyukan da za a kashe kuxin a kansu ne.[3]

Baqin da aka gayyata daga ko ina a Arewa don zuwa Kaduna su mutum dubu shida(6,000) ne. Haka kuma dawakai, dudu biyu(2,000) za a kawo don wannan babban biki. Yawancin baqin da dawakan har ma sun iso Kaduna a yanzu haka. Irin cikar da Kaduna za ta yi a wannan lokaci, ba ya misaltuwa. Mun dai san mutanen da aka gayyata, amma ban da Allah ba wanda ya san waxanda za su zo don kansu.

Saboda baqin da aka gayyata, an gina wani gari musamman a Gabas da Sabon Garin Kaduna. Garin an yi shi layi layi, kuma kashi kashi, gida goma sha biyu, wato kowane lardi da nasa. Haka kuma aka shirya rumfunan dawakai daki daki. Don amfanin wannan gari an gina kasuwa da wurin sham magani da kuma asibitin dabbobi. An sa lantarki da famfo a ko'ina layi layi. Garin nan an gina shi da zana ne kuma a cikinsa akwai bukkoki misalin dubu huxu(4,000) waxansu

---

1 *GTK*, 18 ga Janairu, 1956, shafi na 7

2 *Ibid.*

3 *Ibid.*

bukkokin an yi su don mutum xaya ne, waxansu don biyu, waxansu kuwa sa iya xaukar mutane ashirin.

Kafin wannan sansani ya tashi ya zama gari kamar yadda ke yanzu, karka tona irin aikin da aka yi, su tattara zana da gwafofi da igiya da sare dajin don yin tituna da haqa ramin sa famfo da sa sanduna da wayoyin lantarki da tattara itacen wuta da dai makamantansu.

Kafin in yi nisa, bari ku san irin tanadin muhimmin abu, wato abinci, don ximbin mutanen da za su zo wannan gari. Saboda rage wahala da kuma hana tsadar kayayyakin abinci, hukuma ta tara kayayyaki da yawa a yanzu haka. Misalinsu, shi ne daga Kano an kawo ton xari da tamanin(180) na dawa da ton xari(100) na shinkafa. Daga Abuja an kawo ton Saba'in(70) na doya. Haka kuma an kawo galon xari takwas (800) na man ja da galon xari huxu(400) na man gyaxa daga Kano. Wajen nama kuwa gwamnati ta sawo shanu da yawan gaske suna nan. 'Im mun koma can ga sansanin nan da aka yi, za mu ga tilas sai an yi shiri sosai na zaman lafiya da tafiya da al'amura da raba kayan abinci kamar da ma can garin ya zauna nan.

Haka kuma an yi shiri na maganin gobara tun da ya ke wannan gari duk na zana ne, lalle a ji tsoron wuta, a yi shirin maganinta. Tsare mutane da dukiyarsu da kayan adon dawakai daga sharrin varayi, shi ma abin da za a yi tanadi ne. Ko da ya ke zama a wannan gari gajere ne, kuma da ma an san a irin wannan taro a cikin gajeren lokaci, tilas ba za a sami jin daxi kamar a gida ba, amma duk da haka an yi qoqarin a ga cewa baqin nan sun ji daxin zamansu daidai gwargwado.

gwamnatin Jihar Arewa ta tsara masaukai, domin irin baqin da ba a gayyata ba, sa'anan na sun je Kaduna, ba su sami masaukaiba. Masaukan nan suna Arewacin hanyar da ake kira Junction Road, inda ta haxu da Constitution Road.

An shirya wuraren kwanciya, domin mutane misalin xari biyar ko xari shida. An kula da tsabtar wurin sosai. Akwai su masasai da ruwan famfo, har ma an yi wa wurin 'yar unguwar lardi lardi. Misalin su Kano, Katsina Barno da dai sauran sunayen lardunan domin mutanen da suka je. [1]

Firimiya Alhaji Ahmadu da sauran Ministocinsa sun ziyarci sansannin da aka shirya, inda za a sauki dubban mutane da dawakan da za su haxu a Kaduna a lokacin zuwan Sarauniya da mijinta. Sun ga dubban turakan da aka yi wa dawakai, da masallatai da rumfunan masu kashe gobara. Ministan lafiya, Alhaji Yahaya Madakin Ilori, ya zaga xakin maganin da aka yi domin baqin nan. Firimiya ne jagoran wannan qasaitaccen biki don haka ya zo ya ga masaukin baqi don an ce gami ya kori ji.[2]

---

[1] GTK 25 ga Janairu, 1956

[2] *Ibid*., shafi na 7

Wajen raba yawan mutanen da za su zo daga kowane lardi, an yi shi ne akan yawan jama'a na kowane lardi. Yawan mutane da dawakai da za su zo daga kowane lardi da nisan tafiyan da za su yi don su zo su gaida Mai martaba Sarauniya.

Mutane da za su sami alfarmar zuwa ganin Sarauniya daga ko ina a Arewa za su zama iri iri ne. Waxansu tsofaffi waxanda sun san zuwan Turawa qasan nan waxanda kuma sun daxe ba su je ko ina daga garinsu ba, waxansu kuma samari ne, waxanda saninsu na da ne, sai dai abin da suka karanta a tarihi, waxanda kuma don tafiya da ganin duniya har Ingila sun je. Waxansu masu zuwan sai sun taka da qafarsu, waxansu a dawakai, waxansu a mota da jirgi. Daga ko ina dai mutane za su zo da irin kayayakinsu na gargajiya da irin shigarsu na al'ada da makaxansu da dai sauran irinsu.

Mu je ga babban bikin da kowa ke xoki ya gani. Jihar Arewa tana niyyar ta fi kowace jiha, kai hatta hedkwatar Nijeriya, Ikko, wajen nuna wa waxannan manyan baqi cewa muna da al'adu na xaukaka da bajinta, da kayan ado, da na alatu, da mulki, da ban girma, da qasaita da abin nunawa duk irin namu tun tun tuni.

A ran 3 ga Fabrairu, wata qungiya ta zavavvun 'yan dokana lardunan Arewa za su raka motar Sarauniya zuwa fillin sukuwar Kaduna, inda za a yi qasaitaccen hawa wanda a Arewa ba a tava yi ba. Kafin Sarauniya ta iso, mutanen nan 6,000 da dawakan nan 2,000, za su zama suna filin. Za su yi sahu sahu 12, qungiyar kowane lardi suna sahu xaya. Da zuwan Mai martaba za ta zagaya a motarta a sannu, ta bi qungiyoyin nan xai xai da xai xai, sa'an nan ta duba holin soja da na 'yan sanda da na 'yan doka. Bayan wannan sai ta je ta hau dakalin da aka yi mata.

Sa'an na sai qungiyoyin na na lardi lardi xai xai su fara tafiya suna wucewa ta gindin dakalin, su zagaya su koma inda suke a tsaye, waxansu a kan dawakai, waxansu a qasa. Haba, malam, a nan ne za ka ga shiga ta ado, wadda ba ka tava gani ba. Kowace qungiya da kaxe-kaxenta da bushe-bushenta za ta yi iyakar qoqarinta ta nuna ta fi ta sauran abin nunawa.

Bayan duk waxannan sun qare zagayawa sun koma sun tsaya, an natsa, sai kuma badokai 150, waxanda za a zava musamman su taso su kawo wa Sarauniya jafi.

Duk wanda ya je filin sukuwar (ba fa ciki ba, wannan sai wanda aka gayyata) ya tsaya daga waje a kan wani tudun qasa da aka yi don sauran jama'a 'yan kallo zai ga abin bai wa jikokinsa labari in Allah ya yi masa tsawon rai.

Kashegari a wannan fili sarrauniya za ta ga holin 'yam makarantun Arewa 4,000. Za ta zagaya su, su gan ta, ta gan su. Yaran da za su zo daga lardunan Arewa 1,500, sauran kuwa za su zo ne daga Zariya da kuma na cikin Kaduna. Waxannan samari da 'yam mata waxanda Arewa za ta zama a hanunsu nan gaba,

waxanda kuma suka sami sa'ar zave zuwa wannan wuri, Allah ne kaxai ya san murnarsu da xokinsu.

Bayan Sarauniya ta ga faratin 'yam makaranta sai kuma ta tafi *Waitr*, wato ma'akatar duba cutar da qudan tsando ke kawowa ga mutane da kuma dabbobi da magungunan wannan ciwo.

Wannan wuri da Mai martaba za ta ziyarta a Kaduna, shi ne bedkwatar wannan ma'aikata na duk qasashen Afirka ta Yamma guda huxu da ke qarqashin mulkinta. A nan Sarauniya za ta ga ma'aikatan wurin akan aikinsu. Har za ta ga waxansu tsofaffi guda biyu waxanda suka shekara fiye da talatin suna aikin gano qudan tsando da maganinsa. xaya daga cikin tsofaffin nan sau uku ciwon barci na kama shi, ana yi masa magani, amma duk da haka bai bar wannan aiki ba.

Kafin Sarauniya ta qare ziyartarta ta *Waitr*, za ta ga Fulani da shanu lafiyayyu sun taho daga Arewacin qasan nan sun yiwo Kudu don neman ciyawa a farkon shigowar rani, sa'an nan kuma za ta ga waxansu Fulanin da shanunsu waxanda su ke sun qanjame duk sun kamu da ciwo tsando. Waxannan shanu suna nuna irin waxanda su ke yiwo Kudu ne don neman ciyawa a cikin tsakiyar rani. Haka kuma za ta ga malaman shanu suna yi wa waxannan shanu allura, wato 'jagahore' kamar yadda su Fulanin ke faxi. Wannan alamtawa duk za a yi ne don Sarauniya ta gani da idonta irin aikin da wannan ma'aikata ke yi.

Waxannan ranaiku na nan qasa sun zama hutu lokacin da Mai martaba Sarauniya ta ziyarci Arewa: Alhamis 2 ga Fabrairu 1956, Dukkan Jihar Arewa. Asabar, 4 ga Fabrairu 1956. Lardin Zariya da na qasar Kuza. Litinin, 6 ga Fabrairu, 1956, Lardin Binuwai Alhamis, 16 ga Fabrairu, 1956. Dukkan Jihar Arewa.

Waxannan ranaiku, a in ba da hutun su don mutanen Jihar Arewa gaba xaya da kuma na Zariya. qasar Kuza da Binuwai don su shiga cikin shagulgulan da aka shirya game da ziyarar Mai martaba Sarauniya Nijeriya. Mai martaba ta iso Kaduna ran 1 ga Fabrairu, Jos kuma ranarga wata, Makuxri kuwa ran 6 ga wata, da Kano ran 16 ga wata, wanda a wannan rana ce za ta koma Ingila. A Kaduna, za a rufe ofisoshi da qarfe 10 na safe a ran Laraba, 1 ga Fabrairu, sa'anan nan kuma ba za a buxe ranar Jumma'a, 3 ga Fabrairu ba sai qarfe 11 na safe.[1]

Masu Taryen Sarauniya

Ma'aikatan gwamnatin Jihar Arewa har da Ministoci, tare da Gwamna Sir Bryan za su taryi Sararuniya da mijinta a filin jirgin Saman Kaduna. Za su iso da qarfe 12.15 na Yamma. Gwamna zai bi shugabannin nan xai da xai ya sada su da Sarauniya da Mijinta, su gaisa, sa'an nan a xunguma zuwa gidan Gwamna, inda za a sauke su. Ga sunayen shugabannin nan:

[1] GTK, 25/1/1956, shafi na 7

Firimiya Alhaji Ahmadu, CBE, da Sarkin Musulmi Sir, da Abubakar CBE, CMG,da Shehun Barno Alhaji Umar Ibn Muhammad, CMG, CBE; da Sarkin Kano Alhaji Muhammadu Sunusi, CMG, da Ministan Alhaji Aliyu, OBE, da Sarkin Zazzau M. Ja'afaru CMG, CBE, da Cifjoji Mr. Justice T. A Brown; da Ministan Albarkar qasa Peter Achimugu, OBE, da Sarkin Wukari Atoshi Agbumanu, OBE, da Ministan Lafiya Alhaji Yahaya OBE, da Ministan Fidaburdi Alhaji Isa Kaita, da Ministan Ciniki, da Sana'oi Alhaji Aliyu Turaki; daMinistan Kamaru ta Arewa M. Abba Habib, da Ministan Kyautata Zaman Jama'a da Safiyo Shettima Kashim; da Ministan ba da shawara, David Lot; da Sakataren gwamnati K.P Maddocks; Sakataren Kuxi P.H.G. Scott, da Antone-Janar Marshall.[1] A wajen taryen Sarauniya, 'yan Arewa da shugabanni sun nuna kwarjini da isowa waxanda suka baiwa manyan baqi sha'awa da al'ajabi.

Sauka, Jirgin saman na kashe wuta, sai wani shamaki na Sarauniya ya diro ya buxe qofa, aka sanya matakalai da za su sauko; sa'an nan Gwamna da Uwargidansa suka isa qofar jirgin saman, suka tsaya. Ba a daxe ba Sarauniya da Mijinta biye da ita, suka tako matakalai suka aza qafa bisa qasar Kaduna, hedkwatar Arewa. Da saukarsu Gwamna da uwargidansa suka gaishe su. A lokacin ne kuma sojoji suka harba iggwa sau ashirin da xaya. Sarauniya da Mijinta suka hau wani darduma ja, ta isa bisa wani dakali da aka shirya musamman, suka tsaya. A lokacin ne 'yan badujalan Bataliya ta xaya suka yi busan Natioal Anthem, wato Taken qasa.

Sarauniya da Mijinta suka bi dardunan nan, a kanta ne Gwamna ya sadad da Shugaban Sojojin Kaduna da kwamishinan 'yan sanda. Sa'an nan suka duba sojojin Batatliya ta xaya. Sun gama duba sojojin ke nan, sai muka ga lalle Duke yana sha'awar wani burtu da wani soja ke riqe da shi. Sai shi da Sarauniya suka tsaya wurin wannan tsuntu shi ne alamar wannan Bataliya.

Sarauniya da Mijinta suka iso wani dakali da xakin da aka shirya, sai jiragen saman nan 'yan bom, suka wuce suna gaisuwa. Da ta shigo cikin xakin nan, sai Gwamna ya sadad da 'yan Majalisar Zartaswa har da Shehun Barno, Sarkin Musulmi shi ne na farko da aka fara sadawa ga Sarauniya da Mijinta. An yi qasaitaccen shirin karvar wannan Babbar Baquwar Arewa, yadda kowa da kowa baqi da 'yan gari za su san an nuna halin girma da qasaita.

Dubban baqin da aka gayyata zuwa Kaduna, domin ziyarar Sarauniya, gwamnatin Jihar Arewa za ta rarraba musu goron sauka Sarkin Zazzau M. Jafa'aru, da ya ke a qasarsa za a yi wannan taro, shi ne mai masaukin baqin nan, shi gwamnati ta danqawa goron ya rarraba lardi lardi. 'yan kowane lardi za su sami nasu.

---

[1] *GTK* , 25/1/1956,shafi na 1

Yadda aka tsara abin, shi ne in qungiyar mutane ta kai xari uku, to, za a ba su sa guda da buhun goro. In kuwa qungiyar ta wuce hakanan, to, har zuwa xari shida, sai a ba su shanu uku da buhu uku.[1] Saboda sai dubban baqin da suka hallara suka zama cikin farin ciki, murna da annashuwa. Garin Kaduna sai ya xime da gunjin waqe-waqe da kaxe-kaxe. Aka riqa rera waqar maraba da Sarauniya, wadda M. Shehu Alqalanci Sakkwato ya wallafa.

Waqar Maraba Da Sarauniya

Ba shakka wannan shekara.
Ita za mu faxi don ta cira,
Koken da mu kai mun yo gira,
Mun san nasara ba takura,
Mu duk jama'ar Nijeriya.

Domin ku sani Nijeriya,
Wannan tafiya ta Sarauniya,
Tai baqi manyan duniya,
An ji ta a dukkan duniya,
Marhaban da zuwanta Sarauniya.

Wanda anka ji za ta taho mana,
Duka Turawa da Sarakuna,
Da Ministoci in kun tuna,
Duka masu riqon mulkin qasa,
Suka ta da shiri baki xaya.

Aka shirya wuriin da take zuwa,
Da waxanda ka samun gaisuwa,
An shirya tufafi don qawa,
An zavi dawaki don hawa
Da samarin gai da Sarauniya.

Wasu sun yi shiri na wata bakwai,
Wasu nan kusa sunka yi fai da fai,
Ba mai makara a yi kai da kai,
In an zo can a yi xai da xai,
Ta ga namu shiri Nijeriya.

[1] GTK, 25 ga Janairu, 1956.

Dukkan an yi kira a Nijeriya,
Ta Arewa zuwa na Sarauniya,
A Kaduna a zo wokaci xaya,
Bari in zana maka xai xaya,
Ga shirin tariyarta Sarauniya.

Ka ji lardin Sakkwato ne xaya,
San nan na Kano su ke biye,
Haka Barno da tasu bataliya,
Daga nan sai lardin Zariya,
Sun zo tariyar ta Sarauniya.

Adamawa sun zaka hakanan,
Katsinawa sun zo nan da nan,
Haka Bauci da Neja don ku san,
Lardin Binuwai da Ilori don,
Gurinsu ganinta Sarauniya.

Da qasar Plateau lardin kuza,
Sun yi sauri sun zo maza,
Domin su taho su yi girgiza,
Ba a keve mata ko maza,
A cikin murna ta Sarauniya.

Tun ran da mutum shi ke duniya,
Bai ga taro nan Nijeriya,
Tamkar taro na Sarauniya,
An tabbata kowace nahiya,
Sai sun zaka sun ga Sarauniya.

Daga Ikko Kaduna take zuwa,
Bayan ta tashi a nan kuwa,
Sai jiha ta Gabas bari mantuwa,
Ita dai jama'a ka kururuwa,
Da maraice kaza haka safiya.

Wasu don ita ne suka hau bisa,
Wasu motoci suka ja qasa,
Domin tsananin nisa nasa,
An xau wasu kan jirgin qasa,

Domin tariya ta Sarauniya.

Wasu ko sun hau matasa'iku,
Wasu don haka sun hau basikul,
Da zuwanka Kaduna ka gan su ful,
Wasu guntaye wasu ko dabul,
Duk sun yi maraba da Sarauniya.

Ranar gamuwa da Sarauniya,
An kwan da shiri haka safiya,
An tashi da tsari xai xaya,
Kowa na son shi ga ta biya,
Ga dukkan jama'ar Nijeriya.

Ikko Gwamna-Janar na Nijeriya,
Da Ministoci na Nijeriya,
Da Wakilan qullin duniya,
Su ke tariyarta da aniya,
Ga dukkan halussan Nijeriya.

Da zuwanta Kaduna da ta tsaya,
Suka gaisawa da Firimiya,
Ga Gwamna nan Nijeriya,
Ta Arewa gami da mazan jiya,
Ce Amirul Mumini kun jiya.

San nan jama'a su yi tsagiya,
Ta biya ta gane su ta zagaya,
San nan mabiyanta suna biya,
Ba shingi ba wata kariya,
Mai kare ganinta Sarauniya.

San nan ta bi wannan sansani,
Ta ga soja na babban kamfani,
Ta ga 'yan doka wannan yini,
'yan sanda babu batun sani,
Sun yo xamara ta Sarauniya.

Bayan haka sai tsarin dina,
Da maraice shirin ga na Gwamna na,

Kuma da nan ne in kun tuna,
Taka leqo ta ga yanke na,
Da Mijinta a gai da Sarauniya.

San nan gayya ta Firimiya,
Shan ti don kyautata aniya,
Ta yi taxi kan Nijeriya,
Daga nan daxa, sai a yi godiya,
Da zuwanta a nan Nijeriya.

Ya Allah kai ne ka iya,
Jama'armu ta nan Nijeriya,
Mu ga sun dawo mana lafiya,
Su yi bankwana da Sarauniya,
Da salama lami lafiya.

Ziyarar Sarauniya ya qara qawata garin Kaduna, ta fuskoki daban-daban. Firimiya ya xauki alwashin ganin wannan muhimmiyar ziyara, ta zama abu "Mai Farin Ciki, Mai Sa Yin Alfahari," ga kowa. Domin kuma wannan ziyarar ta zama tambari, sai Firimiya ya ce:

> *A yanzu kam duk al'amarin ya sauya, saboda haka dukkammu muka tsaya tsayin daka, cewa sai mun shirya ba da mamaki, wadda da wuya kafin a sami wanda ya shafe mana zane. Muna so mu nuna wa Sarauniya abin kallo na sha'awa, don girmamawa, wanda ba za a iya cewa na Nijeriya ne, ko na Nijeriya ta Arewa kaxai ban e, sai dai ya zama gagara koyo ko'ina.*[1]

A cikin jawabinsa na saqon Sabuwar Shekara, Sardauna ya qara jaddada wannan buri a game da ziyaran nan ta Sarauniya. Ga abin da ya ce:

"Bari mu nuna irin biyayyarmu da girmamawarmu gare su, cikin halin natsuwa da kwanciyar rai, ba tare da rikicin siyasa ko faxan 'yan gida ya ta da hankali ba. Bari su sami ganimmu, su riqa tunawa da mu kan cewa mu ne mutanen qasan nan wadda kan jama'arta ke haxe tamkar 'yan'uwan juna ne, ba ma su qin juna ba, saboda siyasa. Kuma mu ba baya mu ke ba, ba kuma mutanen banza ba ne. Bari mu tabbatad da cewa Mai Alfarma Sarauniya ta bar qasan nan cike da tunnnin kyawawan abubuwa ma su xore wa na Arewa a zuciya tata".[2]

---

[1] Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 196

[2] *Ibid*., shafi na . 196 -197

Sir Bryan Sharwood Smith, shi ne gwamnan Arewa kuma shi ne wakilinta domin haka shi ne zai saukar da Sarauniya. Saboda haka abin ne ma ya samu, ai don aiki aka sa masa Mai Wandon Qarfe, to, ga gawurtaccen aiki a gaban sa. Nan da nan sai aka shiga shirye-shirye yin ayyuka da za su qawata garin Kaduna sosai. Sir Bryan, ya samu Sardauna wanda ya yi daidai da shi wajen aikin nuna qasaita da karimci. Mista Bruce Greatbatch, wanda ya tava yin aiki da Mai Wandon Qarfe, kuma sakataren Sardauna a wannan lokaci, shi aka danqawa al'amurran yin shirye-shiryen nan. Aka kuma tanadi komiti iri iri a Kaduna da za su taimake shi, don a sami sauqin tafiyar da aiki sosai.

Garin Kaduna ne cibiyar tafiyar da ayyukan komitocin da aka kafa a larduna, an kuma qara ma su ma'aika ta sosai, domin komai ya tafi yadda aka buqata. An kuma sa ministoci jagorancin waxannan komiti iri-iri. Sardauna, Gamji Mazan qwarai, shi ya shugabanci ayyukan waxannan kwamitocin. Shi kuwa Sir Bryan, madugu uban tafiya, bai sami gindin zama ba, domin ganin komai ya tafi kamar yadda ake so. Ya sa aka yi wa Gidan Gwamnati wani qasaitacen gyara, xaya tamkan da goma.[1]

Likitoci da ma'aikatan lafiya duk sai aiki ya baibaye su fiye da kima. An umarci Turawan Shanu da su tabbatar da cewa dubban dawakan da suka taso wa Kaduna suna lafiya, kuma za su sami isa Kaduna lafiya, ba tare da sun yi ciwo ko rauni ba. Ko kaxan wannan ba qaramin aiki bane. A cikin watan Disamba, 1955 garin Kaduna ya fara cika da lafiyayyu kuma qosassun dawakai ma su harbin iska. Sun kuma xauki matakan hana varkewar ciwon haukan karnuka wato "Rabies."

A wajen kula da lafiyar jama'a kuwa, a nan ma ma'aikatan lafiya sun taka rawar gani. An yiwa wannan ziyara tattalin rigafin cuce-cuce. An kuma sanarwa jama'ar gari da cewa da mutum ya ji rashin lafiya ta soma kama shi, to, ya yi maza ya ba dubagari labari. Akwai qungiyar ma su yin lamba a kowace hanya da ta shigo cikin Kaduna. Duk matafiyin da zai shiga Kaduna sai an duba shi an tabbatar an yi masa lambar riga kafin 'yan rani wato "Small Pox." Idan ba a yi wa mutum lamba ba sai a yi masa nan take.

Garin Kaduna ya cika maqil da ma'aikatan tsaro. An kuma samo qarin ma su kashe wutar gobara da kayan aikinsu don su taimaki waxanda ake da su a Kaduna. Haka kuma duk hanyoyin da Sarauniya za ta bi aka qawata su, da tutoci, da dogwayen qarafan rataya tutoci, kuma akai a kai aka yi ta yin xaurin guga ma su launuka iri-iri.[2] 'yan makaranta dubbai, maza da mata, aka yi ta kwaso su cikin motoci da jirgin qasa ana kawo su Kaduna, domin su yiwa Sarauniya lale marhabin da barka da zuwa Kaduna. A cikin qaramin lokaci sai gari ya cika maqil

---

1 Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 197

2 *Ibid*, shafi na 199

da jama'a da dabbobi, suna jiran bikin Hawan Ban Girma wanda ake kira "Dabar" da turanci.

Sarauniya a Filin Sukuwa

Da qarfe tara da minti goma sha bakwai (10:17am), Sarauniya ta iso tana saye da rigar maraice, da kuma wani xan qaramin kambi da aka caccava masa lu'u'lu'u, ga kuma lamban nan ta "Order of the Garter" liqe. Mijinta kuwa yaci ado cikin kayan jirgin ruwa, shi ma da lambar Order of the Garter liqe. Cikin 'yan rakiyarsu har da 'yan dokan doki na Kano da Katsina. A bayan Sarauniya, akwai motar gwamnan Jihar Arewa, uwargidansa da kuma 'yan sandan farin kaya. A baya da su ga motar buwarorin Sarauniya.

Da isowar Sarauniya, duk mutanen da ke zaune suka miqe, sojojin Bataliya ta Huxu suka yi gaisuwa, sa'an nan 'yan badujala suka yi busar Allah ya taimaki Sarauniya. Daga nan sai Sarauniya tare da Mijinta suka zagaya qungiya-qungiya na larduna a cikin mota. Da ta iso wurin tarin qasan nan da mutane dubbai bisa dubbai suka taru, sai ta miqe a cikin motan nan buxaxxiya tana kaxa wa mutanen nan hannu. Da za ta dawo ma haka ta yi musu.

Da Mai martaba ta dawo mazauninta, sai Mai Daraja Mijinta ya je ya duba sojojin Bataliyan nan. Da an shirya ita da kanta ne za ta kewa sojojin nan, amma tana saye da kayan maraice, saboda haka sai Mijinta ya kewaya a madadinta.

Daga nan fa qungiyoyin lardunan nan suka fara wo maci zuwa gaban Mai martaba. Ta farko a cikin tsarin ita ce qungiya qasar Kuza. Wannan qungiya tana da mutane dari uku da hamsin da dawaki talatin da huxu. Cikinsu akwai mutanen Miyango 'yan wasa, suna xaure da bante, kowanne da gatari riqe, suna rawar yaqi, abin gwanin ban sha'awa. Su duka sun shafe jikinsu da mai sai qyalqyali su ke yi.

Kowace qungiya idan za ta wuce, takan nuna irin al'adunta da kuma irin tufafinsu. Bayan qasar Kuza, sai Kaba, Binuwai da Ilori. Amma da yawa daga cikinsu ba su saba da hawan doki ba. A cikin taron Tiv ne na cikin qungiyar Binuwai wani ya sulluvo kan doki, har sau biyu.

Da qungiyar Neja ta iso, aka fara ganin gwanayen mahayan dawaki. Abin mamaki ko da ya ke Etsu Nupe bai daxe da tashi daga rashin lafiya ba, amma duk da haka shi ma ya hau.

Bayan Neja sai qungiyar Zariya. Sarkin Zazzau Jafaru yaci ado da wata babbar riga shuxiya-shuxiya, ya kuma yava wata alkyabba da aka yi mata ado da azurfa-azurfa, ya wuce gaban Sarauniya ana bushe-bushe. Kowace qungiya ta iso inda Sarauniya ke zaune, sai Sarakunan da ke cikinta su zaburo, su yi xan sagaraftu su yi wa Sarauniya jin-jina.

Can kuma sai ga Sarkin Katsina Usman ya tunkaro, yaci ado cikin wata farar alkyabba mai ban sha'awa. A qungiyar Katsina akwai dawakai xari uku da mutanen xari shida da sittin da kuma waxansu raquma da ke xauke da tambura.

Sarki kuma na riqe da wata wuqa, xaya daga cikin kayan sarautar Katsina. A gabansa ga dawakan zage, har da wani doki da aka lulluve shi da riga, ga jikansa Bashir a bisa. Cikin wannan qungiya kuma akwai Sarkin Daura, amma shi bai hau ba, sai xansa magajin gari ya hau maimakonsa.[1]

Hawan Ban Girma

Sarauniya da tawagarta sun sauka a garin Kaduna lafiya. Sun kuma iske garin cike maqil da dubban jama'a da 'yam makaranta da dawakai. Kowa cike da farin ciki da zuwanta. A wannan ziyara ta ga jama'a, abin kuma da take so ke nan. Jama'a kuma sun ganta ido da ido. A duk inda aka bi da ita, sai ta ga xaruruwan jama'a suna murna da zuwanta, suna kuma kaxa mata hannu irin na nuna murna da maraba. A wannan lokaci an shirya a yi mata Hawan Ban Girma, hawa na qasaita irin na Sarakunan Arewa, wanda ba kamarsa a duniya.

A wannan lokaci, Sarkin Zazzau Jafaru shi ne kan gaba don shi ne Kwamandan filin. Sir Bryan shi ke kujerar gaba na motar Sarauniya, ya na nuna hanya. Direba kuma ya na tuqa su titi titi, na Filin Daba.[2] Sir Bryan wanda shi ne Wakilin Sarauniya kuma Mai Masaukinta, a lokacin wannan ziyara ya yaba wa 'yan Arewa matuqar gaske. Saboda kyawo da qasaitar wannan biki, wanda ko shakka babu, ya zama gagara-koyo. Ga abin da Sir Bryan, ya ce:

Da gari ya waye Sarauniya ta hau, muka nufi Filin Daba. Taron sai wanda ya gani! Taron sai wanda ya gani! Aka shiga kewayawa da dawaki, ana yi wa Sarauniya jinjina, irin gaisuwar Arewa ta al'ada ga shugabanni. Kai Arewa ta yi aiki. Sai godiya![3]

Dawakin fin dubu biyu suka yi mata jinjina. Ba mu yi tsammani za a sami wani abu kamar qasaitaccen hawan dawakin da aka yi wa Sarauniya a Kaduna ran Alhamis ba. Wannan rana har abada waxanda suka ga irin abin da aka yi, ba za su manta da ita ba. Ba shakka Arewa ta qwacewa sauran jihohi abubuwa masu ban sha'awa, saboda rangadin Sarauniya. Tun da Sarauniya take ziyarar qasashen da ke qarqashin mulkinta, ba inda aka tava yi mata irin wannan hawa.

ximbin 'yan makaranta da za su taro a Kaduna, duk sun sami Tutar Ingila. Ita za su riqa karkaxawa Sarauniya lokacin da take zagaya su a filin sukuwa. Abin dai gwanin ban sha'awa. A cikin waxannan 'yan makaranta har da Fatima Inno, 'Yar Firimiya da Abubakar Atiku qanen Sarkin Gwandu, a filin sukuwa suna maraba da Sarauniya.[4]

---

1 GTK, 8/2/1956, shafi na 1

2 Bryan Sharwood Smith, *Auren Zobe*, shafi na 83

3 *Ibid*,

4 GTK, 25/1/1956, shafi na 6

Da suka iso wajen gidan ministoci, nan ne Sarauniya da Mijinta suka fara ganin abin da zai zauna musu a arai har abada. Nan ne suka fara ganin jerin dawakai da suka ci ado iri iri. Jerin nan ma dawaki ya kai mil biyu. Masu jaridun Ingila da ke cikin safa wadda aka shirya musu musamman, sai suka ruxe, kowa na so-ya xauki hotuna da sinima. Tilas motar ta tsaya suka yi ta daukar masu dawakan nan har suka gaji. A nan wakilin Gaskiya ya ce musu kaxan ke nan, tun da ba su ga Dabar ba, wanda za a yi kashegari.

Daga baya, Sarauniya da Mijinta suka sauka daga motoci, suka shiga yawo cikin mutane, ba dogari, ba xan sanda ba xan doka.[1] Abin da take so ke nan, don wani daga cikin 'yan rakiyarta ya ce: "Ba'a bin da Sarauniya ke so kamar ta ga jama'arta kuma jama'arta su ganta."[2] Ta kuwa nuna wannan hali na son jama'a. Domin kuwa a lokacin da 'yan makaranta ke nuna ma ta wasan kwaikwayo da ke nuna halin zaman qauye, abin ya qayatar da ita sosai. Ta yi ta gewayawa tana dubu yara kashi kashi, gungu gungu har ma don sha'awar al'amarin da take yi, irin tsawon lokacin da aka shirya za ta yi sa'an nan ta bar wurin, sai da ya wuce kana ta tafi.[3]

Mutane fiye da dubu talatin suka yi kallon dawakai fiye da dubu biyu, da mutane dubu shida, waxanda suka zo daga larduna goma sha biyu na Jihar Arewa. Tun kafin asuba mutane ba iyaka suka haye bisa wani tudu da aka tula qasa, yadda kowa zai iya ganin shagalin da a ke yi a filin nan na Kaduna.

Wajen qarfe biyar na safe dawakai suka yi ta shigowa filin sukuwa suna tsayawa matsayinsu da aka shirya musu. An karqasa lardi lardi ne. Iskan nan na hunturu da a ke fama da shi a daidai wannan lokacin a shekara babu shi sam. Adon da aka cirvaca a wannan wuri sai wanda dai ya gani da idonsa kawai.

An qawata dawakai da ado iri iri, mahayansu waxansu cikin alkyabbu da aka yi wa ado da dusar zinariya, suna qyalqyali. Ba shakka ma raquma sun qara qawata wannan babban hawa. Don Turawa da Baqar Fata da yawa, waxansu ba su tava ganin raqumi ba, sai dai ko a hoto. Idan mutum ya ga 'yan sulke, 'yan lifida da 'yan kwalkwali, sai ya tuna da zamanin da.

Rumfunan da aka shirya su ma sun cika da mutanen da aka gayyata, Turawa da Baqar Fata. Cikin rumfan nan da Sarauniya za ta zauna ga Sarkin Musulmi Sir Abubakar da Shehun Barno Alhaji Umar Ibn Muhammadu El Kanemi, su duka sun ci ado cikin fararen kaya da alkyabbu, sa'an nan ga Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Ahmadu Sardaunan Sakkwato, yana saye da riga nan mai adon zinari-zinari, ya aza wata alkyabba da aka yi mata ado da dusar zinariya. Su duka suna

---

1 Bryan Sharwood Smith, *Auren Zobe*, shafi na 83

2 *Ibid*, shafi na 82

3 Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 201-202

fuskantar taron dawakan nan, waxanda su ke alla-alla su ga isowar Mai martaba Sarauniya da Mai daraja Mijinta.

Sir Bryan bature ne wanda kusan ya fi sauran Turawa sani da cuxanya da 'yan Arewa. Ya kuma daxe a Arewa, kusan ba lungun da bai shiga ba. Amma babu shakka ya yi alfahari da wannan rana mai cike da tarihi, ya nuna farin cikinsa maras isani da cikakkiyar murna. Ba shi kaxai ba har duk wanda ya taimaka wajen cimma nasara. Amma babu wanda zai fi Firimiya farin ciki da wannan rana, a dalilin haka ne ma ya ce:

To, bisa gaskiya mu kam a qasar nan, ba shakka mun cika da xoki, lokacin da mu ke jiran isowarta. Kai har ma shekaru da suka wuce bayan ziyarar, da dukkan abubuwan da suka auku cikinsu, irin yadda muka riqa ji tamkar dai yadda muka ji ne a lokacin ziyarar nan tata. Ba mu kuwa qi ta sake ziyararmu ba, in har da hakanan xin za ta samu. Mun yi alfarma mun kuwa yi farin ciki. Wannan kuwa ba tamu ce mu 'yan kaxan da, wato kamar ni da abokan aikina kurum waxanda suka sami ikon saduwa da Sarauniya a Birnin London, a'a, har ma da dubban mutane da ke yi mata sanin raqumin yara, wato nesa da nesa, amma fa ba wanda bai san ta ba a hotuna da sinima. Tunanin cewa ga shi za ta zo har nan tsakan – kanimmu, ita da kanta, abu ne wanda bai misaltuwa, kuma ba a cewa game da godiya sai hamdala.[1]

Daga qarshe dai Sarauniya da Mijinta suka shiga gungureriyar motan nan da aka tanada saboda wannan sha'ani. Motar fa buxaxxiya ce yadda kowa zai sami sukunin ganinta sosai. A kan hanya mutane dubbai suka yi dafifi suna yi mata maraba ciki ma har da 'yam makaranta da aka jerra su kusa da filin jirgin sama.

Sarauniya a Majalisa

qarshen abin da Sarauniya za ta yi a Kaduna, shi ma muhimmi ne ga wannan jiha. Shi ne ziyararta zuwa Majalisar Arewa, inda wakilan Majalisar Arewa da Sarakunan Arewa za su haxu a xakin shawara na tunawa da Gwamna Lugga.

Sarauniya Elizabeth ta Biyu, da Mijinta Duke of Edinburgh, sun ziyarci *Lugard Hall*, inda suka sadu da wakilan Majalisar Sarakuna da na Majalisar Wakilai. Sarauniya kuma ta amsa jawabin biyayya, wanda Mai girma Alhaji Ahmadu Sardaunan Sakkwato, Firimiyan Jihar Arewa, ya yi mata.

Mai martaba ta je xakin shawaran nan da Yamma ran 3 ga Fabrairu a mota. Da isarta bakin ginin sai ta duba faratin soja inda ta karvi gaisuwar sarauta. Sa'annan da isarta bakin qofa gwamnan Arewa ya taryeta, ya shigar da ita da Mijinta cikin Majalisar.

Da zamanta a kan kujerar shugaban Majalisar, sai Mai girma Firimiyan Arewa Alhaji Ahmadu, sardaunan Sakkwato, ya tashi ya karanta mata jawabin ban

[1] Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 200

girma, sa'an nan a miqa mata jawabin, ita kuma ta mai da jawabi. A cikin jawabinsa ya ce, "kowannenmu ya yi na'am da ziyararku".

Jawabin Firimiya

Mutane fiye da arbaminya da aka gayyata suka cika filin qofar *Lugard Hall* ran Jumma'a, a lokacin da Sarauniya za ta ziyarci haxaxxen taron Majalisar Sarakuna da na Wakilai. Wannan karon ma Sarauniya ta ci ado da wata doguwar riga da aka lallabe ta da gwal, akanta kuma ga wani xan qaramin kambi, sai kashe ido ya ke yi. Mijinta kuwa ya yi shigar kayan jirgin ruwa ne.

Da Sarauniya ta iso kofar *Lugard Hall*, sojoji yam badujala suka yi busan gaishe ta. Lokacin da ta shiga Majalisa ta zauna, sa'an nan ta ce su ma su zauna. A hagun Sarauniya ga Mijinta, da jakadiyarta. A damarta kuwa ga Gwamna da shugaban Majalisar Wakilai Mr. C.R. Niven.

Ana zaunawa sai Firimiyan Jihar Arewa ya miqe, ya yi dogon jawabin biyayya cikin turanci da Hausa. Da ya gama ya miqa mata cikin wani rago na fata da aka qasal shi ita ma ta miqa wa bawansa sasa'an a shi kuma buwata ya miqa mata ta jawabar da za ta yi. Da ta gama abin sai M. Umaru Gwandu aka a Majalisar Dokokin Jihar Arewa ya fasara da Hausa.

Daga nan sai Sarauniya da Mijinta suka hau benen *Lugard Hall* suka karvi gaisuwar mutane dubbai da ke waje suna son ganinta.

Da ta kama, gwamma ya sadad da manyan Sarakuna goma sha biyu na kowane lardi da ba a sadad da su ba a da, da kuma wakili daya daga kowane lardi.

Jawabin Firimiya ya ce:

"Zuwa ga mai mafificiyar daraja Sarauniya Da yardarki ya Mai martaba: Mu mutanen Jihar Arewa ta Nijeriya muna son mu gaishe ki, gaisuwa ta bayyanad da irin dagewar ban gaskiyarmu ga gadon sarauta a wannan ziyarki ta farko ke da mai daraja a jiharmu ta Nijeriya ta Arewa. Ya Mai martaba, haqiqa na yi sa'a bisa maqamin na Firimiyan jihar Arewa da aka ba ni damar bayyana miki irin tsananin biyayya wadda mu mutanen Arewa ke da ita a gare ki.

"Dukanmu mun karanta labarun tafiye-tafiyenki a waxansu qasashen nan a kan daman mu da da kika ba su ta su nuna biyayyarsu. Mun yi ta fata da gaske cewa za ki sami damar ki ziyarci qasar da take ita ce ta fi girma da kuma yawan mutane a cikin Afirka. Haqiqa muna godiya bisa ga darajantawar da kika yi mana.

"Ina farin cikin shaida miki ya Mai martaba da kai mai daraja, cewa kowannenmu ya yi na'am da labarin ziyararku cikin murna da farin ciki. A jihan nan muna da al'ada ta gargajiya ta yin biyayya ga Sarakunanmu da shugabanninmu. Muna girmama abin da na gaba suka yi. Saboda haka ina iya

tabbatar miki ya Mai martaba, cewa dukkan irin biyayyar da aka nuna miki ba ta zahiri ce ba kawai, ta kai har zuci.

"Muna da qwaqqwaran dalili da ya sa mu murna. Ba wai kadai kan damar da muka samu ta gai da Elizabeth ta Biyu ba, wadda bisa yardar Ubangiji take Sarauniyar haxexxiyar qasar Birtaniya da Arewacin Ireland da kuma sauran qasashen da ke qarqashin mulkinta, shugabar qasashen da ke zumunci da Ingilan matsariyar addini da dai dukkan ma'anar da ke ga manyan sarautocin nan, a'a sabe da ganin gawurtatta, wadda ta gaji Sarakuna da sarrauniyoyi, waxanda suka yi gudummawa da yawa a kan haxa xiyarcin duniya a cikin lokuttan wahala da yamutsi.

"Ba don irin misalin da ke kika bayar ba, da kuma mutaqaddiminanki masu son xiyanci, da har abada ba su gama kansu da sauran masu son xiyancin ba, kan su tserad da duniya daga masu son vantashe su ba.

"Muna iya tunawa, ba daxewa, a shekarun da suka shige irin wannan haxarin da ya tashi don muna xaya daga cikin sarqan nan ta haxa kai, wadda ita ce kawai ya tsarshe mu daga halaka; mihimmin abu ne a tuna cewa ba don haxa kan nan da muka nuna ba a lokacin, da maganar ci gaban shirin Mulki da qara arzikin qasa ba za a yi su ba yanzu. Irin gudummuwar da sojan Afirka ta Yamma suka yi game da qare faxa haqiqa ta kawo sakamakon alheri.

"Ya Mai martaba, wataqila kina sane da cewa jama'arki masu biyayya a gare ki a cikin jihan nan sun kai miliyan 18, waxanda suka bazu a kan qasar da girmanta wajen sikwaya mil 280,000 ne. Mu jiha ce mai mutane da yawa.

"Nijeriya ta Arewa yadda take a yau ta faru ne ta qaddarar tarihi da jaruntakar shahararrun kakannimmu da kuma tsinkayar ma'aikatanki, waxanda na gaba da ke suka aiko qasan nan. Har yanzu mu mutanen ne masu yawa da addinai dabam dabam. Mafi yawammu Musulmi ne, da yawa Kirista ne, da dama kuma a suna bin waxansu addinai.

"Har yanzu dai muna da aikin haxa mutane dabam dabam a cikin al'ummarmu don su zama abu guda. Har wa yau dai muna da aikin haxa kai, wanda ya ke wajibi ne, don a kau da rashin amincewa ta fuskar qabila ko addini, a mai da kyautatawa, hanqurewa da girmama al'adun juna a madadinsu. Muna neman haxa kai, amma ba na tanyon shanu ciri ba! Irin misalin da kika bayar ya amfane mu qwarai.

"Jawaban da ki kan yi na Kirsimati, waxanda mun sani mutane ne qasashe da yawa na saurarawa, waxanda suka haxu a bisa abu xaya-shi ne biyayya ga Sarauniya, ya zama abin da burimmu ya fuskanta. Mun san irin tsananin girmamawar da ki ke da ita ga duk waxanda ke tsoron mudalaqin iko, suna kuma gaskata cewa xiyauci na tsaruwa kawai ta irin hanyar siyasa ta dimoquraxiyya. Duk da haka kin tsere ma siyasa-alamar haxa kai ke nan, wadda dukkan mutane

za su fuskanta idan gardandami da rashin jituwa suka nemi halakar da rayuwar jama'a.

"Ya Mai martaba, shahararren wakilinki na jihan nan – gwamnanmu ya nuna mana cewa ba za a iya riqon qasa ta alwashi da daxin baki ba, amma ko an yi shawarwari waxanda ba su da daxi masu kawo baqin jini, wajibi ne masu mulki su karvi dukkan sakamakonsu. Ni da abokan aikina muna koyi cewa tafiyad da gwamnati ta hanyar zamani tana da wuya. Muhimmi ne mu fahinci wannan da ya ke mun kusanto lokacin qara sake Shirin Mulki.

"Mutane ne masu alfahari, Sarakunammu da ma'aikatansu tuni da ma suna da gogayya a kan tafiyad da sha'anin mulkin en'e. Saboda haka, al'ada cewa, kawai ya kamata mu himmatu kamar yadda da yawa waxansu mutane na cikin qasashenki na zumunci suka himmatu, mu qara xaukar nauyin tafiyad da sha'anonimmu. Mun sani a bisa inda aka fito cewa ministocinki da wakilanki ba za su sa wata qaya ba a hanyarmu – haqiqa za su ba da duk irin taimako da qarfafawar da su ke iyawa.

A cikin tawali'u muna addu'a mulkinki ya Mai martaba ya zamo mai tsawo da kwarjini kuma yaci gaba da albarkatuwa da babban farin ciki, wanda irin nagartarki mai qayatarwa ga qasashen zumunci ya cimcimta. [1]

Sarauniya ta ga Shugabannin Arewa cike da kwarjini da haiba. Ta ga nuna karamci da mutunci irin na al'adun jama'a masu daraja kuma abin alfahari. Sardauna ya yi jawabinsa yana mai nuna fahimtar luggar turanci irin na Sarakunan Ingila. Ya yi jawabi mai ma'ana ya kuma nuna zalaqa mai ban sha'awa da kwarjini mai sa natsuwa. Daga nan sai Sarauniya ta ba shi amsa :

Jawabin Sarauniya

"FIRIMIYA: Ina Farin ciki qwarai da na zo nan yau na karvi jawabinka kuma in yi magana da kai da kaina. Irin abubuwan da ka faxa na biyayya sun qayatad da mu qwarai. Irin maraban da ka yi mana ni da mijina a nan jihar Arewa ya nuna mani cewa irin biyayyan nan da soyayya akwai su ga dukkan kowaxanne qungiyoyi na jama'a.

"Da yawa waxanda suka zo, don su gaishe mu, sun yiwo tafiya mai nisa, waxansu a bisa dawaki, waxansu kuma a qafa. Muna so kuma a issad gaisuwarmu ga dukkan waxanda ke cikin larduna, waxanda ba su samu daman zuwa nan ba, da waxanda ba za mu samu ganin su ba a wani wuri a cikin jihan nan.

"Bayan abin daya haya kaxan bisa shekara hamsin na mulkin ingilishi, qasarku yanzu tana kusa ga samun mulkin kai. A cikin shekarun nan an yi sakiya, wadda aka samu ba da wani tsanani da wahalce-wahalce ba. Ya dace cewa a

[1] GTK, 8 ga Fabraru, 1956, shafi na 4

cikin wannan xaki, wanda aka ambaka da sunansa, ya kamata mu tuna da Lord Lugard da kuma dukkan waxanda suka yi gudummuwa ga wannan gawurtaccen ci gaba – maaikata waxanda suka suka zartad da adalci ba da son zuciya ba kuma tare da aiki da Sarakunan jihan nan suka shimfixa harsasun kyakkyawan gwamnati – haka kuma da Mishan, malamai da ma'abuta fanni, waxanda suka kawo amfane-amfanen da kuma qaruwar arziki ta hanyar ciniki ga jihan nan.

"Ina so kuwa im ba da yabawa ta ga irin abin da mutanen jihan nan da kuma dukkan Nijeriya suka yi a cikin yaqe-yaqen nan biyu na duniya. Ba za mu mance manyan qungiyoyi na mayaqan da jihan nan ta Arewa ta aika ba, musamman wajen yaqin habasha da na Burma.

"Har yanzu dai akwai saura da yawa abin da za a yi. Yaqi da jahilci da cuta da talauci za su bukaci himmantuwarku da aikatawarku shekaru da yawa nan gaba. Na yi murna qwarai da jin da yadda ministoci, en'e-en'e da dukkan waxanda abin ya shafa suka tasam ma waxannan rikitattun matsaloli. Irin niyyan nan da ke bayyane ta mutanen jihar Arewa, ta sa 'ya'yansu makaranta ta qayatad da ni. Im ba ta haka ba, rayuwar arziki, wanda ya ke wajibi ne ga ci gaban qasa ba zai samu ba.

"Ilimin matashi ma muhimmi ne qwarai. Ina farin ciki qwarai da jin irin abubuwan da kuka rigaya kuka yi, da kuma shirye-shiryen da kuka yi saboda wannan.

"Mutanen Jihar Arewa sun sha bamban da wajen xabi'a al'ada da addini. Kome irin bambancin da ke akwai na game da addini, ina roqonku ku tuna, cewa su irin gaskace-gaskaccen nan suna tushen ababen gwaji na al'umma game da adalci da kyawon hali. Na tabbata cewa gwamnatin Jihar Arewa ko yaushe za ta ba mutane xiyancin su bauta wa Ubangiji ta hanyar da ra'ayin kowa ya zavam masa.

"Haqure wa juna wajibi ne ba game da abubuwan da suka shafi addini kaxai ba, har ga waxanda ra'ayuyuka da al'adu suka bambanta. Ta irin fahinta, junan nan ne kawai mutane da ke da al'umma daban-daban da qabilu, za a iya zama abu xaya.

"Ina tabbatar muku da tsananin sha'awa ta a cikin sha'aninku da kuma ci gabanku, wanda zan ci gaba da lura da shi qwarai. Ina roqon albarkar Ubangiji ta sauka ga qasan nan da mutanenta."[1]

Sarauniya ta yaba wa jama'ar Arewa duka, ta yaba irin tsarin da Arewa ta yi, domin karvar baquntarta, ta yaba wa Turawa da Baqar Fata, waxanda ke riqe da hidimomin Arewa, ta kuma yaba wa rundunonin Arewa, waxanda suka je yaqin neman 'yancin duniya a Habasha da Burma.

---

[1] GTK, 8 ga fabrairu, 1956, shafi na 5

Da ta waiwaya kan sha'anin tafiyad da mulkin Arewa, ta ce bayan 'yan shekaru hamsin da 'ya'ya a qarqashin mulkin Ingilishi, ga shi "qasarku yanzu tana kusa ga samun mulkin kai. A cikin shekarun nan an yi sakiyar hanyar mulki, wadda aka samu ba da wani tsanani da wahalce-wahalce ba". Ta ce ya dace, da ya ke ana cikin xakin majalisan nan, a tuna da Lord Lugard wanda aka sanya wa xakin sunansa.[1]

Liyafa a Gidan Gwamna

Mai martaba Sarauniya ta ci Abincin dare da manyan mutane Da qarfe xaya da minti ashirin dai Sarauniya ta isa gidan Gwamna, masaukinsu. Da dare kuma Sarauniya da Mijinta sun ci abincin dare tare da waxannan manyan mutane: gwamnan Jihar Arewa da Uwargidansa, da buwarorin Sarauniya mutum shida da ma'aikatan Gwamna, da Sarkin Musulmi, da Sarkin Kano, da Sarkin Zazzau, da Sarkin Wukari, da Firimiyan Jihar Arewa, da Ministan qaruwar Arzikin qasa, da Ministan Lafiya qasar Kamaru, da Ministan Kyautata Zaman Jama'a da Safiyo, da Ministan Sana'o'i da Ciniki, da Pastor David Lot, da Babban Cifjoji da Uwargidansa, da Babban Baturen Sojojin Kaduna da Uwargidansa, da Sakataren Mulki da Uwargidansa, da Shugaban Majalisar Wakilai, da Antone-Janar da Sakataren Kuxi.[2]

Bayan Wannan qasaitacciyar dina, wato liyafa sai kuma aka shirya wata qwarya-qwaryar biki inda mutane kamar dubu aka gayyata bayan an gama hawan Dabar a ran Alhamis. An yi wannan taro da maraicewajen qarfe biyar inda mutane kusan dubu xaya da aka gayyata don shaye-shaye da sauransu suka cika gidan Gwamna. Wurin da aka shirya sha'anin nan yana da ni'ima. A gefe xaya 'yam badujalan soja suna ta aikinsu. Kowa ya kure adaka yana alfahari da shi xan Arewa ne wata jiha mai bambanci da ban al'ajabi.

Can ba a ankara ba kowa na ta taxe taxe da juna, sai ga Sarauniya da Mijinta sun fito suka hautsuna cikin baqin da aka gayyata. Gwamna shi ya raka Sarauniya, uwargidan Gwamna kuwa ta raka Duke of Edinburgh. Mutane da dama Turawa da Baqar Fata sun yi ta taxe-taxe da su. Waxanda aka nuna wa Sarauniya suka yi taxe-taxe da su, su ne Sarkin Kwantagora, da Sarkin Argungu, da Sarkin Gwambe, da Sarkin Lapai, da Sarkin Yawuri da Lamixon Mubi.

Waxannan mutane ma sun yi taxi da Sarauniya su ne: Malam Tobi Yarafa, da Abba Jatau, da Mr. C.V. Williams da Uwargidansa, da Dr. Mackenzie da Uwargidansa, da Bishop Mort, da Malam Bello xan'amar, da Mgr. Redington, da Mr. G.U. Ohikere, da Alhaji Ahmad Pategi, da Mr. J.E Davies da Uwargidansa,

---

1 GTK, 8 ga fabrairu, 1956, shafi na 5

2 *Ibid*. 8/2/1956

da Alhaji Shehu Abubakar, da Waziri Alhaji Ibrahim, da Mr. P.C. Chambers da Uwargidansa, da Mr. MacBride da Uwargidansa, da Wazirin Ilori, da Leftana Kanar Reid da Uwargidansa, da Malam Audu Anace, da Ciroman Haxeja, da Ibrahim Demsa, da Mr. J.R. Lockie, da M. Sambo Sarkin Fadan Zazzau, da Mr. Macdonald da Uwargidansa.

Mijin Sarauniya, Duke of Edinburgh kuma ya sami damar taxi da waxannan; Sarkin Daura, da Sarkin Misau, da Abdullahi MaiKano Sarkin Wase, da Galadima Boyi Hakimin Gwoza, da Malam Kalia Mongunu, da Mr. Mare da uwargidansa, da Mr. Wreford da Uwargidansa, da Alhaji Abubakar Imam, da Rev. Mother Gregory, da Mr. W.M. Briston, da M. Bello Magajin Rafin Gwandu, da Alhaji Shehu Buhari, da Mr. E.G. Gundu, da M. Umaru Gwandu, da Mr. T.E. Letchworth da Uwargidansa, da Dr. R.R. E. Jacobson, da Mr. C.W. Michie da Uwargidansa, da Michael Audu Buba, da Malam Bashar Daura, da Mr. Gunn da Uwargidansa, da Mr. Hunter da Uwargidansa, da Mr. Muhammadu Kabir, da Manjo Sir Henry Farrington da Uwargidansa.[1]

Sarauniya ta Raba Lambobi

Bayan da Sarauniya da Mijinta suka koma cikin gida, sai aka shirya lambobin da za ta rataya wa waxanda suka samu. Daga nan ta jim kaxan sai fito ta shiga raba lambobin girmamawa. Sarkin Musulmi shi ne na farko. Amma shi tuni aka rataya masa tasa lambar. Ya zo gaban Sarauniya ne ta aza masa takobi bisa kafaxa kamar yadda take yi wa dukkan manyan mutanen da suka sami lambobin zama "Knighted", wato zama "Sir" kenan.

Waxanda ta rataya wa lambobi (ko liqawa) su ne; Alhaji Haruna Sarkin Gwandu lambar C.M.G., da Mr. C.V. Williams, C.M.G., da Dr. S.G. Wilson, C.B.E., da Manjo H.E. Wilson, O.B.E, da Alhaji Shehu Ahmadu Madakin Kano O.B.E., da Dr. C.M. Ross O.B.E da M. Muhammadu Sarkin Fika, O.B.E., da Abdullahi MaiKano Sarkin Wase, M.B.E., da Malam J.Y. Inusa, M.B.E., da Malam Gwamna Sarkin Kagoro, M.B.E.

Sauran waxanda ta liqawa lambobin M.B.E. su ne: M. Dada Kwoi, da H.V. Eyre, da Mr. F. Y Carrena, da Mr. J.F. Hindle, da Leftana-Kanar G. N. Dennis, da Mrs. Freda Miles, da Malam Dogo (Sarkin Jaba a da), da Malam Muhammadu Lawal Wazirin Zariya, da Malama Kubura, da Malam Abubakar Madawakin Sakkwato, da Mr. H.G. Fildes da Malam Sa'idu Alao.

Waxanda ta rataya wa tambobin da a kan ba Sarakuna su ne; Malam Abdu Aguye Sarkin Koton qarfe, da Malam Ibrahim Sarkin Kanem, da Malam Ologbonyo Obaro na Kaba, da Malam Muhammadu xan Bici (Kweri) Sarkin Wamba, da xan Tudu Sarkin Dabai.

---

[1] GTK 8/2/1956, shafi na 8

'yan sanda da sojoji da ta liqawa lambobi su ne: Manjo W.J Martin O.B.E., C.S., da Yako Yerwa, B.E.M, da Mr. A.C.C. Peebles, Q.P.M., da Mr. W.E. Rumbelow, Q.P.M., da Mr. W. Ford, C.P.M, da Mr. E. Everett, G.P.M., da Manjor J.J. O' Sulliban, M.B.E., da C.P.M, da Samanja Usman Doba, C.P.M.[1]

Tana gamawa sai `yan bajudala suka yi kixan Allah ya taimaki Sarauniya, daga nan kowa ya watse..

Liyafa a Gidan Shawara

Amma kuma bikin da ya fi qayatarwa, shi ne wanda aka yi a Gidan Shawara wato "*Lugard Hall.*" Sarauniya ta Ziyarci Gidan Shawara inda ta sadu da Sarakuna. A wannan lokacin liyafa ce, Firimiya Sir Ahmadu Bello ya bayyana godiya da girmamawa ga Sarauniya. A cikin jawabinsa har ya ce:

"Wadda mu ke ganin nan, ita ce mashahuriyar da ta yi gadon gidan sarautar Sarakuna da Sarauniyoyi, waxanda suka yi taimako qwarai wajen haxa kan 'yantacciyar duniya. Muna iya tunawa, sosai sosai kuwa, irin haxurra na shekarun baya, lokacin da kasancewarmu cikin qungiyar makekiyar abotan nan, ita ce ta hana mana shiga babbar halaka. Abu ne wanda ya ke muhimmi, a tuna da cewa da a yau ba za mu sami yin maganar ciyar da tsarin mulki gaba ba, da qara qaruwar arziki, im ba domin haxa kan nan da muka yi ba.

"qaddara irin ta tarihi ita ce ta zama sanadin kafa Nijeriya ta Arewa, da qwazon mashahuran kakannimmu, da tsinkayar gaba ta ma'aikatanki, waxanda ainihin waxanda kika gada suka aiko da su zuwa qasan nan. Abin da ya rage mana mu yi, shi ne mu harhaxa al'amurran da ke warwatse don su zuma abu guda. Muna neman haxa kai, amma ba zama irin abu guda ba."

"Ni da abokan aikina mun fahinci cewa sha'anin mulki irin na zamanin nan abu ne mai wuya. Mu mutane ne ma su alfarma ba da fariya ba, kuma Sarakunammu da ma'aikatansu sun daxe da goguwa cikin sha'anin mulki. Don haka ne ya zama wajibi cewa ya kyautu mu qara dagewa kan zama cikin shirin xaukar nauyi fiye da da game da tafiyar da ayyukammu".

Sarauniyar kuma ga abin da ta ce a cikin jawabin amsar da ta bayar:

"Bayan fiye da shekara hamsin kaxan a qarqashin mulkin Turawan Ingilishi, qasarku yanzu ta tasam ma karvar mulkin kanta. Daidai ne mu tuna da cewa ma'aikatan gwamnati waxanda hulxa tasu tare da Sarakuna ne ta sa aka sami kafa mulki mai kyau bisa harsashi mai qarfi. Mishan da malamai da ma su ilimin yin sana'o'i su ne suka shigo da fa'idodin da na qaruwar ciniki ga jihan nan."

"Yaqin da a ke ta yi da jahilci, da cuce-cuce da talauci, za a yi shekaru ana ta bukatar himmarku da qwazonku. Na yi mamakin irin ganin dagewar da jama'a suka yi don su sama wa 'ya'yansu ilmi. Idan babu , ba za a sami kyautata qaruwar

[1] GTK 8/2/1956, shafi na 8

arziki ba. Bai wa mata ilmi, shi ma babban abu ne . Na yi murna da jin irin qoqarin da kuka yi da kuma hanyoyin da kuka tanada don gaba a game da wannan."

"Na kuma tabbata gwamnatin Jihar nan ko yaushe za ta bar jama'a su yi addinin Ubangiji irin wanda ransu ya xaukar ma su. Haquri da juna wajibi ne, ba kuwa a kan sha'anonin addini kaxai ba, har ma a tsakankanin waxanda ra'ayoyinsu da al'adunsu suka bambanta. Ta wannan hanyar fahintar junan kaxai ce a ke iya haxa kan jama'ar kabilu iri iri wuri xaya."[1]

Haqiqa wannan ziyara ta mai Alfarma Sarauniya, munhimmiyace kuma bukukuwan da aka yi sun ba kowa sha'awa da alfahari. Don haka ne gwamnan Arewa Sharwood Smith ya yi alfahari da ganin yadda aka karrama wannan baquwa saboda ya ce "Arewa ta yi qoqari!" Bayan da Sarauniya ta ziyarci gidan Shawara inda ta gana da Sarakunan Arewa, sai aka kuma gayyaceta, wata qasaitacciyar liyafar cin abinci a xakin taro na *Lugard Hall*.

A lokacin wannan liyafa ne, Sardauna ya sami lokaci kuma a tsanake, ya kalli Sarauniya sosai, har ma ya misalta ta, kamar haka:

Ta karanta wannan a cikin Majalisa wadda ke shaqe da jama'a, ga kuma zafin lantarki na gaggan fitilun da aka buxe a cikin kwararon nan na xakin. Ni da nake na saba da zafi, amma tilas in cewannan na fitilun na ji shi sosai, amma ita Sarauniya ko ta nuna alamar akwai zafi ba ta nuna ba. Sai wani sheqi da haske take yi sai ka cewata la'asariya ce ta lokacin damina a fadarta ta Windsor.

Lu'u-Lu'u da jauharorinta sai qyalqyali su ke yi cikin hasken fitilun nan, sai ka cewalqiya idan ta faxa kan ruwan tabkin da ke kaxawa. Kyakkyawan adon nan da ta yi, kayan qawa sun zuba ko'ina sun baibaye ta tamkar ruwan da ke gangarowa daga kan dutse. Ba mu tava ganin wani abu mai kama da wannan ba im ba don akwai iyakantaccen lokaci ba, da ba mu qi mu yi ta zama a wurin ba har magariba muna ta xebe qwarqwatar ido.[2]

Malam Magaji xambatta Wakilin jaridar Gaskiya ta fi kwabo a hedkwata ya sami lamba,Mai martaba Sarauniyar Ingila Elizabeth ta Biyu,ta aiko masa da wannan lamba mai daraja.Wannan lamba ana kiranta "Lambar Tunawa da Ziyarar Sarauniya Nijeriya a shekarar 1956".A cikin takardar da aka aiko haxe da lambar, Mai martaba ta ce ta yaba da qwazon malam Magaji da qoqarinsa,waxanda ta tabbata sun taimaka ainun wajen nasarar ziyararta.

---

1 Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na .202-203

2 *Ibid*, shafi na 203

Tun ranar da Sarauniyar ta sauka qasan nan, suke tare da M. Magaji domin shi ne ya wakilci jaridun Gaskiya da Nigerian Citizen wajen ba da labarin ziyararta. Ya bi Sarauniya a jirgin sama duk inda ta ziyarta a qasan nan.[1]

M. Magaji xambatta ya nuna qwazo da qwarewa wajen aikin jarida, ya kuma kawo bayanai da labarai dalla-dalla a kan wannan muhimmiyar ziyara. Babu shakka ya cancanci yabo saboda ya taimaka gaya wajen kawo labarai da hotuna da za su taimakawa masu bincike akan tarihi sosai.

'Yan rakiyar Sarauniya, ayari ne mai yawa. Amma 'yan rakiyarta makusanta masu kuma yi mata hidima ba su wuce mutum biyar ba. Jakadiyar Sarauniya Countess of Euston: Ita ke kula da xakin barcin Sarauniya Kwamanda D. Steele-Prekins CVO, RN: Shi ne likitan Sarauniya da mijinta. Kwamanda Richard Coville CVO, DSO, RN: Shi ne Sakatare mai ba da labaran sha'anin Sarauniya. Leftanan-Kwamanda Micheal Parker, MVO, RN : Shi ne Sakataren mijin Sarauniya. Leftanan-Kanar Right Hon. Sir Micheal Adeane, KCB, KCVO: Shi ne Sakataren Sarauniya.

A wata karramawa da yaran Arewa suka yi wa Sarauniya Elizabeth, Babbar Baquwar Arewa, sai suka aikowa 'ya'yanta da muhimmiyar kyauta. Waxanda suka miqa wannan kyauta su ne, Umar Ka'oje xan shekara goma sha biyar daga Sakkwato, da wata yarinya 'yar shekara goma sha uku mai suna Yachella, 'yar Wazirin Barno, su ne suka miqa "kyautar yaran Jihar Arewa" zuwa ga 'ya'yan Sarauniya, wato Prince Charles da qanwarsa Princess Anne. An ce jawabin da Umaru ya yi a wannan taro, ta injin mai qara sauti ya ba kowa sha'awa.[2] Sarauniya kuma ta karvi wannan kyauta don ta kaiwa 'ya'yanta cikin farin ciki.

A lokacin ziyarar Mai martaba Sarauniya ba ta ci tuwon dawa miyar kuka ba, ba ta kuma sha fura da nono ba, ba ta kuma sha fate ba. Abin mamaki duk lokacin da Sarauniya ke zaune a Kaduna a kan kai mata madara da kirim daga gonar ma'aikatar gona a Shika ta lardin Zariya. Kullum sai an tabbata madarar da kirim xin tsarkakakku ne kafin a aika zuwa masaukinta a gidan Gwamna.[3]

Lokacin da Sarauniya take rangadin Nijeriya, an shirya wani tsohon soja yana riqe da tutar Sarauniya, yadda dai mutanen Nijeriya za su gane Sarauniyarsu na wurin. Wannnan tuta a duk inda Sarauniya ta ziyarta, Samanjan soja mai suna, Mamman Zinder, babban Odalen Gwamna-Janar shi ne zai riqe ta.

Shi kuwa Mamman Zinder a 1928 ya shiga soja a Zariya sa'an nan ya yi yaqin Is'afirka da na Burma Ya samu lambobi dabam dabam guda bakwai ne ya samu wajen nuna jaruntaka har da ta Hali mai Kyau. Cikin 1946 ya yi ritaya daga aikin

---

1 GTK 27/3/1956, shafi na 1

2 *Ibid.*, 8/2/1956

3 *Ibid*, shafi na 8

soja, a lokacin aka naxashi Odale a gidan Gwamna na Ikko. Cikin 1953 ya samu lambar aza kambi na Sarauniya Elizabeth ta Biyu. Ita tutar Sarauniya da zai riqe an yi ta ne da siliki, an kuwa zayyana ta sosai. A kan tsinin sandarta akwai kambi na azurfa da zaki.[1]

Sarauniya ta ga qasaitar 'yan Arewa da halin girma ta ga kuma al'adu na jama'a daban-daban waxanda suka ba ta mamaki da al'ajabi. Da ta kammala ziyararta a Kaduna sai ta nifi Jos, Inda ake so ta huta da kwararniyarjama'a na wani xan lokaci. Sarauniya ta kawo ziyara a Jiha mai bambanci da bam mamaki.

Sarauniya a Garin Jos

A ran 4 ga Fabrairu ne Sarauniya za ta bar Kaduna zuwa Jos inda daga nan jirgin saman Jos za ta taho a mota zuwa Tudun Wada Jos inda za ta sauka. Bayan kwana biyu a Jos za ta tashi a jirgin sama zuwa Jihar Gabas ran 6 ga wata. Akan hanyar ne za ta tsaya a Makurdi. Ran 16 ga Fabrairu, za ta iso Kano akan hanyarta zuwa gida. Za ta yi kamar sa'a biyu a Kano. Inda za ta je Nasarawa gidan Razdan, daga nan ta tafi zuwa cikin gidan Sarki ta qofar Nasarawa. Bayan ta fito daga birnin ta qofar Mata ta wuce zuwa filin jirgin sama.

Jama'a da yawan gaske waxanda ba su sami zuwa Kaduna ba, za su iya ganinta a waxannan garuruwa da za ta ziyarta. Kuma ko da ya ke lokacin da za ta vata a waxannan wurare qurarru ne, duk da haka bikin da za a yi sai wanda ya gani. An kuma shiryi gidan rediyo ya bayyana wannan ziyara saboda jama'a su ji duk abin da ake yi, a ko'ina Sarauniya ta ziyarta.[2]

Ran Asabar, ranar da Sarauniya ta tashi zuwa Jos don ta huta, an jera dawaki da 'yan Sanda da 'yan doka kamar yadda aka yi a lokacin da za ta sauka Kaduna. Da qarfe tara da rabi na safe (9:30am) gwamnan Jihar Arewa da Uwargidansa suka nufi Jos a jirgin sama.

Malam, a filin jirgin saman nan, jiragen sama goma sha huxu ne har da na Sarauniya suka hallara. Na Sarauniya kuwa 'yanSanda sun kewaye shi suna gadi. Masu jaridu suka shiga jirage huxu daga ciki zuwa Jos, inda kuma suka taryi Sarauniya a can. Da qarfe tara Sarauniya da mijinta da buwarorinta suka baro gidan Gwamna zuwa filin jirgin sama, suka iso da qarfe tara da minti arba'in.

Bayan da Sarauniya ta isa filin jirgin sama, sai ta yi bankwana da 'yan Malisar Zartaswa. Sa'an nan ta bi darduman nan da aka shimfixa zuwa wurin jirgin samanta. Muqaddashin Gwamna da Firimiya suka raka ta. Da ta isa ta yi bankwana da su. Da qarfe goma daidai jirgin sama ya tashi, ya isa Jos da qarfe sha xaya saura minti goma. A nan gwamnan Jihar Arewa ya sadad da Cifjoji Hurley

---

[1] GTK 1/2/1956, shafi na 10

[2] *Ibid*., 25/1/1956, shafi na 9

da uwargidansa, da Mr. A.T. Weatherhead da uwargidansa, da Malam Rwang Pam, Sarkin Jos da uwargidansa.

Sarauniya ta shiga mota, ana tafiya a hankali, mil takwas a cikin a wa guda, aka bi ta hanyar Vukur zuwa Tudun Wada. Nisan wurin kamar mil biyar ne daga filin jirgin sama.

Da qarfe goma sha xaya da minti goma mijin Sarauniya, Mai Daraja Duke of Edinburgh ya ziyarci wajen aikin Kuza na Delima. A nan rasdan ya sadad da Mr. Hinton, Janar Manaja na Gold and Base Metals. Mr. Hinton kuma ya sadad da Mr. L. Parmer, Sakatare, da Mr. I.L.C. Gibb; manajan kewayen wurin, da Mr. H.J.L Newton, babban injiniya.

Mai daraja kuma ya ziyarci Harwell. A nan aka sadad da Manjo Wilson, Janar manaja na Kamfanin A.T.M.N. gare shi. Shi kuma ya sadad da waxannan mutane gare shi: Mr. J.L Farrington, mataimakin Janar Manaja, da Mr. D. Sharples, mai kula da sashen Arewa, da Mr. Punnet, mai ba da shawara. Daga nan ya koma Tudun Wada.

Ran Lahadi Sarauniya da mijinta sun yi addu'a a Majami'a ta St. Pirane. A nan Gwamna ya sada Rt. Rev. J.L. Mort ga Sarauniya da Mijinta. Da qarfe 9:45 na safe Sarauniya da mijinta suka shiga jirgin sama zuwa Enugu amma sai da suka tsaya a Makurxi. Da ma Gwamna ya riga ya yi gaba ya sauka a Makurxi. A nan Gwamna ya sada Razdan na lardin Binuwai da manyan mutane goma ga Sarauniya da mijinta. Sarauniya da mijinta suka shiga motar Jeep, suka riqa bi kusa da ximbin mutanen da suka yi dafifi a filin jirgin sama. Da qarfe 11.20am suka yi ban kwana da Gwamna suka nufi Enugu.[1]

Da Sarauniya ta bar Kaduna, jama'a sun yi ta jin kaxauci saboda rubuwa da ita, alhali kuwa kwana uku rak ta yi a wannan gari. Daga nan ta tafi Jos inda ta xan shaqata kafin ta wuce Enugu, sai da ta bi ta Makurxi. Daga Enugu sai ta sauka a Birnin Kano.

Sarauniya a Birnin Kano

Bayan kamar kwana goma, Sarauniya ta dawo Arewa a kan hanyarta ta komawa gida, ta dakata a Birnin Kano na awa shida, don a shirya ta je Fadar Sarki da misalin qarfe biyar na Yamma. A wannan lokaci sai Sarkin Kano Muhammadu Sunusi ya ce yana bukatar, in Sarauniya ta yarda ta shiga cikin gida wajen iyalensa. Sarauniya ta yarda, Matar Mai Wandon Karfe Lady Sharwod Smith ta yi ma tafinta, a lokacin da ta sadu da iyalen Sarki. Daga Fada, sai aka nufo cikin birni da Sarauniya.

[1] GTK 8 ga Fabrairu 1956, shafi na 8

A wannan rana Birnin Kano ta cika maqil da dubban mutane, waxanda suka shaqe titi titi. Sarki kuma ya sa an kawo dawakai da mahayansu daga kowace qasar Hakimi, wanda ya baiwa Sarauniya sha'awa sosai. Sir Bryan ya ce:

"Muka nufo gari, muka iske gari ya cika maqil, ga dawaki fiye da arba, dubu huxu an jera. Ga rundunar raquma. A ganina mutun fiye da rabin miliyan suka taru a Birnin Kano ran nan, suna kaxa wa Sarauniya hannu, irin na murna".[1]

A wannan rana yawan dawakin da ke Kano, sun ninka yawan dawakan da aka tara a Kaduna don Hawan Ban Girma.[2] Dubban jama'a kuma sun sami ganin Sarauniya, ga ta ga su. A cikin wannan ziyara, Sarauniya ta duba makarantar 'Yam Mata. Aka kuma shirya mata ajin yaqi da jahilci a qofar Fada, inda Alhaji Ahmadu Coomasie, babban jami'in yaqi da jahilci na Jihar Arewa ya bayyana mata wannan aiki.

Tirkqashi! Dubi duk irin shirye shiryen da aka yi a Kaduna inda dawakai fiye da dubu suka yiwa Sarauniya jinjina, amma sai ga shi Jalla Babbar Hausa ta share mata zane. Haxa dawakai da raquma fiye da dubu huxu wani abu ne gagara koyo. Tun daga wannan lokaci ne aka sallamawa Kano; cikin awa shida Hawan ban Girman da ta yi sai ya zama tambari. Tun daga wannan lokaci ne duk wani babban Bature, idan ya zo Nijeriya sai ya yi zakwaxin son yaje Kano ayi masa Hawan qasaita.

Ba Zan Manta da ku ba

gwamnan Jihar Arewa Sir Bryan Sharwood-Smith, ya sami saqo daga Mai martaba Sarauniya Elizabeth. Saqon kuwa game da ziyararta Arewa ne. Ga yadda saqon wanda ta aiko a ran 6 ga Fabrairu 1956, a inda tace:

> *Daga Sarauniya da Jama'arta Don Sir Bryan Sharwood-Smith. Tashinmmu daga Makurxi yau, ni da mijina mun aiko muku da matuqar godiyarmu gare ka da gwamnatin Nijeriya ta Arewa, don saboda marhaban mai bam mamaki da kuka yi mana a lokacin ziyararmu duka.*
>
> *Ko da ya ke ba mu samu damar daxewa ba ko mu ga da yawa a cikin babbar Jihan nan taku kamar yadda muqa so, Kyakkyawan hawan nan na Dabar a Kaduna, wanda ba za a manta da shi ba, ya hana mu ga mutane na daga ko'ina a larduna.*
>
> *Muna godiya gaya game da shirye-shiryen da ya sa wannan ya yiwu, sa'an nan muna duban lokacin da za mu ziyarci Kano nan gaba.*

---

[1] Bryan Sharwood Smith, *Auren Zobe*, shafi na 84

[2] Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na 204

(Sa hannun) Elizabeth R.

Mai girma gwamnan Jihar Arewa ya ba da amsa a haka
7 Sa Fabrairu, 1956

Zuwa ga gwamnan Enugu.

A isad da saqon nan ga Mai martaba,

Saqonki mai alheri wanda na karanta wa Majalisar Gudanaswa ya shiga rammu sosai. Ko da ya ke qungiyoyin dawakai sun watse, sanin cewa, da yawa daga cikin talakawanki masu biyayya za su saqe yi muku maraba tare da mai daraja a qasar Arewa a Kano, shi ya sauqaqe damuwanmu na rabuwanku da mu. Na ida aikina na biyayya ga Mai martaba.

(Sa hannun) Sharwood-Smith

Gwamna.

Ran Jumma'a motar Sarauniya yar lagwada, wato Rolls Royce, aka tafi da ita Kano, don ta jira Sarauniya da Mijinta a can.. Abubuwan da ta gani a zuwanta Birnin Kano , sun qayatadda ita sosai. Sarauniya da mijinta suna mamakin bikin Kaduna sai ga na Kano wanda ya qayatar sosai.[1] Lalle, Arewa Jiha ce mai bambanci da bammamaki. Irin wannan kara da karamci da Sarauniya da ayarinta suka gani ai har abada ba za su manta ba. A dalilin haka ne Babbar Baquwa Elizabeth ta sake aiko da saqo na musamman a lokacin jawabinta na bankwana. Inda ta ce:

"Lokaci fa ya yi,wanda lalle ne in ce muku sai wata rana.Yau misalin mako uku kenan da ni da mijina muke ta tafiye-tafiye cikin qasarku,muke ta ganin abubuwan kallo mabambanta,da mutane da al'adu waxanda suke su ne Nijeriya".

Wannan shi ne farkon kalamin Sarauniya Elizabeth ta biyu,lokacin da ta yi jawabin,ban kwana ran sha biyar ga Fabrairu 1956,daga gidan Gwamna Janar a Ikko,rediyon Nijeriya ya baza maganar zuwa ko'ina a cikin duniya. Tace,"a ko'ina muka je, akan zarce har zurfin zuciya, wannan abu kuwa ya sanya mu farin ciki matuqa. A koyaushe za mu riqa tunawa tare da godiya, godiya, irin kirkinku da lafiyarku.

"Jama'ar Nijeriya sun yi maraba da ni da murya xaya,ina fata wannan zai taimake ku ku qara samun gama kai da junanku".

---

[1] GTK 15/2/1956

"Na san, wannan ziyara ta jawo qarin aiki mai yawa ainun ga mutane da dama,sabili da haka ina buqatar amsar sa hannu cikin irin shirye-shiryen da aka yi.

"Ma'aikatan gwamnati da waxanda ba na gwamnati ba,soja,'yan sanda,'yan doka,kamfanin relwe,da kamfanonin Jiragen sama,dukansu ina gode masu domin qoqari da suka yi na mara asani tare da cikakken tunani da duban abin da ya ke dai-dai,sa'ad da suke aikace-aikacen nan nasu.

"Babu wani wanda zai ziyarci Nijeriya,a cikin waxannan lokuta na motsawar abubuwa,da zai kasa gane irin himmar da dukkan sashen jama'an nan su ke da ita.Wannan irin buqata ta son kyautata abubuwa,da kowa da kowa ke ambata wa,ya ba ni matuqar sha'awa.

"A kowace sa'a wadda wani canji zai auku a cikinta,a ko'ina ne kuwa a cikin duniya,a kan sami wahaloli-wani lokaci ma har akwai vacin rai-amma ina fata zumunci tsakanin 'yan Nijeriya da Ingilishi a nan,zai inganta samuwar shekaru masu yawa na kyakkyawan ci gaba.

"qaruwar arziki kurum a kanta,ba ta isa ba.Wannan abu ma muhimmi ne ya zama halayyarmu ta yau da kullum a rayuwar mu a cikin masarufi,a cikin sana'a,a cikin aikin gwamnati,a cikin gwamnati,sun cika kusantar abin buqata.Wato aminci, mutunci da gaskiya.Im ba mun tabbatad da waxannan kyawawan halaye ba,ba za'a samu cin amfanin ilimin kimiyya ba.

"To, yanzu ina so in yi magana ne musamman ga ma'aikatana,waxanda suka qetaro ruwa suka zo aiki a Nijeriya.Na sani a cikin waxannan lokutai masu sassauyawa,waxansun ku suna fuskantar waxansu abubuwa da suka dame su,tare da matsuwar zuciya.Amma fa har yau kuna da muhimmin aiki da za ku yi a wajen kyautata zaman wannan babbar qasa.

"Haqiqa naji daxin irin aikin da kuke yi qwarai,musamman saboda qarfin zuciyarku da rashin son kai da kuka sa a gaba. A wajen yiwa mutanena na Nijeriya aiki,gaskiya ne ni kuka yi wa aiki, zan kuwa cika kulawa da halin zaman ku na nan gaba.

"A yanzu da nake shirin tafiya daga qasan nan,ina buqatan im bar wa dukkan 'yan Nijeriya wani abin kuma da zai riqa tunashe su wannan ziyara,wadda ta za ma qaruwa a garemu,na kuwa tabbata ta qareku.Na shirya cewa daga yanzu har zuwa gaba rundumomin sojan Nijeriya za'a riqa kiransu Sojan Sarauniya na kanta a Nijeriya.

"Ta wannan hanya,zan iya ambata godiya sabili da jaruntaka da biyayya da mutanen Haxaxxiyar Nijeriya,waxanda suka bauta wa qasarsu sosai a zamanin zaman lumana da zaman yaqi.

"Ina domin ku,da domin 'ya 'yanku cewa zamanin da ke tafe zai zo muku da zaman lafiya,ci gaba da arziki."[1]

Da Sarauniya ta qare ziyara, sai aka nufi Filin Jirgin Sama, inda ta yi ban kwana da Arewa tana xaga hannu ana xaga mata hannuwa. Babban Jirgin Saman nan ya yi qugi. Zuwa can ya yi sama cikin duhun dare. Wannan ziyara babu shakka muhimmiya ce tasa kowa yin farin ciki da yin alfahari. An fara ziyara lafiya an kuma gamata lafiya. Sir Bryan ya ce:

Ranan da Sardauna ya nisa sai ya ce "Ba shakka mun gode wa Allah! Tun zowar Sarauniya har ta tashi, 'yan sanda ba su sami labarin wani ya yi wa wani sata ba. Ba su ji labarin wani ya yanke wa wani aljihu ba. Hasali ma dai ba su ji labarin wani mugun aiki ya faru ba."[2]

Rabbon da a yi garramammen gagarumin taro a Nijeriya irin wannan, tun ziyarar da xan Sarkin Ingila ya yi, wato wanda ya zama Sarkin Ingila Edward na Takwas. Lokacin da ya ziyarci qasan nan yana Yarima ne, an a ce masa Prince of Wales. Ya kuwa zo Nijeriya cikin 1925. A zuwan nasa, Kano kaxai ya ziyarta, ita ma ta cikin jirgin qasa ya ziyarce ta daga Ikko. Manyan Sarakuna aka tara don su yi masa maraba ta ban girma.[3] A Cikin Lokacin Zuwan Sarauniya An Sako Mana Baiwar Haxa Kai Da Aniya.

Jawabin Gwamna

"Shugaba da mashawarta, Lokacin qarshe da muka taru a nan shi ne sa'ad da mai Alfarma Sarauniya ta karvi jawabin biyayya daga Firimiya. Don haka ya dace musamman cewa, jawabi na na yau ya kamata ya fara da ambaton ziyaran nan. Mai Alfarma da Mijinta mai daraja sun baqunce mu xan lokaci kaxan, amma duk da haka, kamar yadda dole ne dukammu mu ji a zukatammu, a cikin lokacin nan an sako mana wata sabuwar baiwa ta haxa kai da aniya, ko'ina a jihan nan, waxanda nake fata har abada kaifinsu ba zai dushe ba, kuma ba za su yanke ba.

"Lokacin da muka tuna cewa a nan Arewa, kamar shekaru hamsin da kaxan da suka wuce, babu wani abu sai yaqe-yaqe tsakanin wannan qasar Sarki da waccan, lalle ya isa abin al'ajabi da har dubban mutane da yawa na kowane jinsi da kowacce qabila a cikin jihan nan, duk da bambancin nan nasu wajen al'adu da addini da hanyoyin zama, suka zauna tare cikin zumunci a halayen zaman nan masu wuya na babban sansanin baqin nan da aka kafa a nan Kaduna.

---

1 GTK 22/2/1956, shafi na 7

2 Bryan Sharwood Smith, *Auren Zobe*, shafi na 84

3 *Ibid.*, shafi na 196

"Ina fata wannan ruhu na haxa kai da aniya guda da ya dasu, zai dauwama ya yi yaxo a cikin shekarun gaba, domin kuwa im ba haka ba, jama'ar jihan nan ta Arewa su kansu ba za su dauwama ko su yaxu ba.

"Kafin in ci gaba da ba da salsalar abubuwan nan da ministocina ke nufin yi cikin watannin nan masu zuwa, dole ne da farko in isad da godiyar gwamnati, wadda Firimiya ya riga ya yi cikin jawabin da ya yi a rediyo, ga duka jama'an nan na ko'ina a Jihar Arewa, waxanda suka yi wahala, ba dare ba rana, don su tabbatar da cin nasarar ziyaran nan ta mai alfarma Sarauniya. xaukar wannan babban aiki mai nauyi cikin nasara, a xan gajeren lokaci haka, lalle ya zama abin yabo tutur ga duk waxanda suka ba da gudummawan nan tasu, ko mene ne irin matsayin zamansu a duniya.

"To, yanzu zan juyo zuwa gaba kuma. Ra'ayin gwamnatin Jihar Arewa ne tun da jimawa, cewa bisa yadda jama'ar Arewa ke cin gaba ta fuskar sha'anin siyasa da zaman jama'a da arzikin qasa dole ne a ba kowane lardi, cikin lardunan nan goma sha biyu na jihan nan, iko daidai bakin iyakar tsarin manufar gwamnati, yadda zai qara xaukar nauyin yin al'amuran qasarsa da kansa gwargwadon irin al'adun qasan nan da xabi'unsu na gargajiya, da bukatunsu.

"To, yanzu nufin gwamnatin jiha ne ta kafa hukumomin larduna da za a ba su waxansu kevavvun iko.Su hukumomin nan na larduna, waxanda za su tafiyadda manufar jiha, ba a nufin su naqasa matsayin Majalisun en'e'en'e da ikon majalisun nan, cikin iyakokinsu. Haqiqa ma, za a haxa kan duka harkokin en'e-en'e ne, su zama kamar sarqa tsakanin en'e-en'e ne, kowane lardi da gwamnatin Jiha.

"Garaje ne a yanzu a nemi tsefe bayanin shirin nan filla-filla, don kuwa kowane lardi yana da irin nasa matsaloli musamman. Nufin gwamnati ne ta nemi shawarar gwanaye kan irin wannan fanni, kafin ta auka wa wani tsari takamaimai. Amma duk da haka ana iya cewa nufin dai baki xaya shi ne a kafa kowace hukumar lardi da Razdan da Majalisar da za ta riqa ba shi shawara, wadda za a yi ta musamman da Sarakuna da mashawartan majalisun En'e, waxanda dukansu baki xaya suka yi kowane lardi guda.

"A wannan wuri, ya dace in tuna wa mashawarta abin nan da na faxa a lokacin buxe gamuwar istimat shekara biyu da suka shige, game da sha'anin mulkin larduna.

Idanu ne da Uwa

"Razdan da ma'aikatansa na cikin lardinsa,… wakilai ne na gwamnatin Jiha a qasashen … Aikinsu ne ko yaushe su riqa sanad da ofisoshin ministoloci dabam dabam, da kuma gwamnatin jiha, irin abubuwan da ke faruwa ko ina a jihan nan… Aikinsu ne kuma har yau su tabbata …. cewa ana tafiyard da shirin gwamnatin Jiha, kuma su yi maganin matsaloli na cikin qasa da kuma waxansu lalurori da suka auku… a duk lokacin da suka auku, Wato ke nan dai su idanu ne

da kunnuwa na gwamnatin jiha …. kuma su ne babban damtsenta na dama a duk lokacin da aka nemi ta da hankalin zaman jama'a ko kuma aka far ma yancin mutanen qasa.

"Ma'aikatar Mulki haqiqa ita ce tsaiko mai qarfi wanda duk abubuwa suka dogara a kansa. Don haka wajibcin wannan ma'aikata ba zai qasa yadda ya ke a da ba, nan gaba a shekaru masu zuwa. Lokacin da ... zamani ya zo na yadda jama'ar qasan nan suka yanke shawara cewa sun isa su samu mulkin kai, idan ya zamana ba su gaji tsaikon sha'anin mulki mai qarfi kuma mai gwaninta ba, wanda 'ya'yan Arewa kullum su ke qara cike shi, to, lalle ikon gwamnatin zamanin nan za ta raurawu har ya zaman lardin ikonta bai qetare iyakar babban garin jihan nan ba. To, in ko aka kai ga haka, babu wani abu wai shi Jihar Arewa ke nan.

"Ba nufin gwamnatin nan ne ta rushe tsarin larduna ba. Amma nufinta ne ta faxaxa tushen tsarin nan, ta qarfafa shi, ta hanyar jivinta en'e-en'e da tsarin nan, yadda ta haka musamman, za a tashi tsaye sosai wajen shiryad da tsarin nan ya koma hannun 'yan Arewa xungum.

"Har yau kuma za a kula da tsarin mulkin Majalisun En'e. A yanzu majalisun nan an yi su ne kusan xungum da gogaggun mutane, waxanda suka gaji maqamin nan, ta hanyar al'ada, ko aka naxa su don cancantarsu. Matsalolin nan barkatai, kuma cuxaxxu, waxanda kowacce en'e lalle na fama da su kulluyaumin, sun sa wajibi ne ainun tafiyad da al'amuran nan ya zama yana hannun mutanen nan ne da suka cancanta sabili da gogayyarsu. Amma kuma wajibi ne shi ma a jivinta ma jama'a baki xaya ainun da ala'amuran kowacce en'e, komin qanqantar al'amari da koMai girmansa. Saboda haka gwamnatin jiha tana nufi da sannu-sannu za ta qai hanyoyin zaven 'yam Majalisa, a duk inda aka ga haka za ta yiwu, kuma ya kamata.

"Kamar yadda aka saba za a roqi majalisa a cikin taron nan ta yi tanadi saboda bukatun gwamnati na shekara mai zuwa. Dokar qasafin 1956-57 yana bukatar yin tanadi na kusan fam miliyan 14 da rubu'i, wato qarin fam miliyan guda da rubu'i uku ke nan bisa na shekaran nan mai qarewa,1955-56. qarin nan ya yi daidai da tsarin nan na kuxaxen raya qasa na 1955-1960. Sauran harkokin kuxi da za a gabatar su ne Shirin Neman Rancen gwamnati da a ke son kawowa, da kafawar kuxin Manyan Ayyukan Raya qasa.

"Shirin nan na Neman Rance ya haxa har da amsar kuxin Hukumar Ciniki."[1]

Sir James Robertson, Gwamna Janar na Nijeriya ta sa tubarrakinsa ne akan muhimmancin ziyarar Sarauniya ga qasa baki xaya. Ya ce zuwanta ya jawo wa qasan nan xaukaka.

---

[1] GTK 3/1956, shafi na 4

Qasan Nan ta Samu Xaukaka

Majalisar Nijeriya ta buxe taronta na qasafin kuxaxen da za ta kashe daga shekarar 1956 zuwa 1957. Yadda aka saba dai Gwamna-Janar na Nijeriya, Sir James Robertson shi ya zo, ya yi musu jawabi. Gwamna-Janar ya fara jawabinsa da batun ziyarar da Mai martaba Sarauniya da Mijinta suka yi qasan nan. Ya yaba da irin shirye-shiryen da aka yi game da sauran shagulgula a ko ina cikin qasan nan saboda zuwan Sarauniya.

Gwamna-Janar ya ce irin sunan da Nijeriya ta yi, ta fito fili kowa ya santa, saboda zuwan Sarauniya, ba makawa zai jawo mata qarin xaukaka da qaruwar arziki a duniya. Daga nan Sir James ya gangaro kan maganar taron gyaran Shirin Mulki da za a yi a London cikin wannan shekara.

"Wannan taro muhimmancinsa ya wuce yadda kowa ke zato, domin a nan ne, za a xinke duk wata varakan Nijeriya wajen sha'anin mulki". Gwamna-janar ya yi maganar wakilan da za su wannan taro. Yana fata su zama nagari ne masu kuma hangen nesa.

Daga nan ne Sir James ya juyo wajen maganar Istimat da shirye-shiryen gwamnatin Nijeriya na raya qasa. A nan ne ya yi maganar waxansu kuxi £91,000,000 da gwamnati ke niyyar tanada saboda raya qasa. Gwamna-janar ya ce, "Na sani waxannan kuxi ne musu yawa, don haka ne ministocina suka rarrage kuxin da ma'aikatansu za su kashe a wannan shekara".

Ya tavo maganan nan ta kyautata hanyoyi. Anan ne ya ce kowa ya sani hanyoyi su ne tushen qaruwar arziki. Don haka gwamnati ke da niyyar kashe £51,000,000 ga kyautata hanyoyi kowaxanne iri. Bayan hanyoyi, Sir, James ya gaya wa wakilai cewa gwamnati ta gama shirinta na kyautata gidan waya. Za a daxa aminta gidajen wayar da a ke da su yanzu, kuma za a buxe waxansu a ko ina a Nijeriya da Kamaru ta Kudu.

Wajen al'amarin , Gwamna-janar ya ce gwamnatin Nijeriya a shirye take ta ga al'amarin ya watsu ya kuma inganta. Ya yi magana kan makarantun fasaha da asibitin Jami'a ta Ibadan.

A qarshe Sir, James ya yi wata babban magana game da ba 'yan Nijeriya jan Nijeriya. Ya ce gwamnati za ta naxa wani mutum musamman da za a dauqa wa wannan aiki.

Ya rufe jawabinsa da wani abu da Sarauniya ta ce, sa'ad da take wa wakilai jawabi, inda ta ce, "Na tabbata wannan majalisa ita ce ta alamta cewa Nijeriya qasa xaya ce. Ina fata za ku ci gaba da aikinku cikin natsuwa da zuciya xaya har ku ga qasarku ta yalwata tana kuma kunnen doki da kowace qasa a duniya".[1] Murnar baquncin ziyarar Sarauniya bai kwaranye a Arewa ba qwamfa! Sai ga

[1] GTK Maris 1956, shafi na 6

wata baquwa daga gidan Sarautar Ingila ta kawo ziyara Nijeriya. Wannan baquwa kuwa ita ce Princess Royal.

A qarshen wannan shekarar 1956 ce Nijeriya ta karvi baqunci babbar Baquwa daga Ingila. Sakataren qasa na qasashen da ke qarqashin Mulkin Ingila, Right-Honourable Alan Lennox-Boyd, ya ba da sanarwar cewa Maigirma Gimbiya Royal ta amsa gayyatar da babban gwamnan Tarayyar Nijeriya ya yi mata a madadin gwamnatin Tarayya na ta ziyarci Nijeriya a watan Nuwamba, 1956.

Maqasudin ziyyarar ita ce buxe manyan cibiyoyin ilmi na Nijeriya guda biyu, wato Asibitin Koyarwa a Ibadan da reshen Shalkwata da ke Zariya na Kwalejin Kimiyya da Fasaha ta Nijeriya, da kuma halartar wata addu'a a Anaca domin bikin cika shekaru xari da kafuwar xariqar Cocin Naija.

A shekarar 1957 sai Mai martaba Uwar Sarauniya ta ziyarci wannan qasa. Da zuwanta ba ta yi wata-wata ba, sai ta buqaci ta ziyarci jalla babbar Hausa. Ganuwar nan ta Birnin Kano mai ximbin tarihi sai, ta sake samun tubarrakin 'yar Gidan Sarauta da ke kan ziyara, wato Uwar Sarauniya wacceke kan hanyarta ta ta komawa Ingila daga wata ziyara da kai kai Rhodesia.

Ministoci ashirin kafin lokacin da aka tsara tsohuwarta da qarfe bakwai na safiya, jirgin sama qirar B.O.A.C, Britaniya xauke da Uwar Sarauniya ya tava qasa (sauka) a yanayi na hantsi a filin jirgin sama na Kano a safiyar Laraba. Da jirgin ya sauka ya tava qasa a hankali ya isaya, sai kofar ta buxe Sarauniya ta sauka inda gwamnan Arewa da Uwargidasa Lady Sharwood Smith da 'yarsu Angela suka tarbeta.

Sarauniyar tana sanye da tufafi na qawa, wato fararen kaya da dantofi (siket), haxe da leshi sannan a kafaxarta ta xora wani xan Mayani da aka ci bakinsa da kwalliya da safa dogaye a hannunta, da takalma masu tsini, da 'yar qaramar jaka ta riqewa a hannu dukkansu farare, sai hular da ta sanya da aka yi mata ado a goshi da gashin fiffiken kaza aka yi 'yar toliya da shi.

A lokacin da suke tsaye a kusa da jirgin, Gwamna ya gabatarwa Sarauniya waxannan mutane. Firimiyan jihar Arewa Alhaji Ahmadu Sardaunan Sakkwato, da Sarkin Katsina Alhaji Usman, da Madawakin Kano Alhaji Shehu Ahmadu, da Babban Rasdan na Kano, M. H.A.S. Johnson, da Muqaddashi Mataimakin kwamishinan 'yan Sanda Mr. C. Gidley, da Kwamandan Filin Jirgin Sama, Mr. Weatherell, da Mr. G. Macgregor mai wakiltar BOAC da WAAC.

Sarauniyar ta xau xan wani lokaci tana magana (zantawa) da Firimiya da wakilan Arewa a cikin manyan baqi, sannan ta shiga wata mota Rolls Royce da aka yi jerin gwano da ita, cikin rakiyar gwamnan da babban Sakatarenta Kanar Gillait. A cikin mota ta biyu akawai uwargidar Sharwood-Smith, da mai sarauta Hambledon, da babban Sifeta Wells.

Da Firimiya, da Sarkin Katsina da Madakin Kano suka biyo baya a cikin nasu motocin, jerin gwanon ya bi ta yankin gudanar da hada-hadar kasuwanci, ya shiga birnin ta qofar Mata, ya bi ta Masallaci da hanyar Yamma zuwa masaukin Sarki.

Sun isa fadar da qarfe bakwai na safe cikin busar kakaki da algaita, sannan ba tare da vata wani lokaci ba suka shiga tsohuwar Majalisa tare da Gwamna, da Firimiya da Madawaki da ke wakiltar Sarkin Kano, da sauran manyan baqi inda aka gabatar mata da kansiloli na En-e-En-e. Daga bisani ta koma can ciki tana tafiya a tsakanni mahaya dokuna, da rawunna, da makaxa har zuwa cikin motarta.

Da qarfe takwas saura 'yan mintoci lokacin hantsi ya soma, Sarauniya ta koma filin saukar jiragen sama inda aka tuqata zuwa inda za ta shiga jirgi inda mutane suka taru domin ganinta.

Sannun a hakali ta kai ga bakin jirgi, inda ta yi adabo da bankwana ga waxanda aka gabatar mata da su a can baya, har ta taka matakalar jirgi inda ta sha hannu da Gwamna da Uwargidan Sharhood Smith da Angela. Da ta kai qololuwar matakalar sai ta juyo ta yi murmushi ta xaga hannu tana yi wa kowa bankwana, cike da farin cikin karvar da aka yi mata a Kano da ziyarar da ta kai wannan birnin mai tarihi. Manyan baqi sun yi sahu sun daga mota hannu bibbiyu suna yi mata bankwana, inda jirgin na Birtaniya ya xaga, suna kallonsa har ya soma zama qarami a can sama ind a ya juya akalarsa daga Arewa akan hanyarsa ta zuwa Malta da Landan.[1]

Haqiqa ziyarar sarauniya ta qara xaukaka mutuncin Nijeriya domin ta qara kwarjini a idon duniya. Jihar Arewa kuwa sai ta zama tagomashin Jiha a Nijeriya. Bugu da qari, wannan ziyara ta qara wa giguwar Siya'sa dake tasowa qarfi sosai Saboda qaratowar Mulkin Kai a shekarar 1959 da Yancin Kai a shekarar 1960. Saboda waxannan dalilai sai Kaduna Hedkwatar Arewa ta dulmuya cikin siyasa, jama'ar garin kuma suka taso suka yi hovvasa wajen fuskantar qaluben siyasar Nijeriya.

[1] Citizen, 542, Asabar 20 1957.

KASHI NA SHA-SHIDA

Kaduna a Siyasar Farko

Tasowar Guguwar Siyasa

'Yan Nijeriya musamman 'yan Arewa sun taimaka gaya wajen taimakon qasar Ingila a yaqin duniya na biyu, wanda ta samu galaba a kan qasar Jamus da qawayenta Japanawa da Italiyawa a shekarar 1945. A lokacin da ake gwagwarmayar shirin yaqi da Jamusawa kuwa, qasar Ingila sai ta yi ma qasashen da ke qarqashin mallakar mulkinta alqawarin samun 'yanci tare da walwala, da raya qasa da jin daxin jama'a, idan har suka taimaka aka qurmushe Jamusawa da qawayenta.

To, amma bayan galabar da Ingila ta samu wajen yaqi da waxannan qasashe suka taimaka ta samu, sai kawai Ingila ta juya baya ga alqawarin da ta yi tun da farko, sakamako kuma shi ne farkawar jama'a ga yin kishin kansu da samun wayewar kai a fuskar siyasa. Ta hanyoyi daban-daban kuma sai suka riqa nuna dagewa a kan lallai Ingila ta ba su 'yancin kansu.[1] To, sai wannan gwagwarmayar neman 'yanci ce ta tada guguwar siyasa a Nijeriya.

Arewa da tafi kowace jiha zaqewa wajen ba da taimako da nuna bajinta wajen yaqi sai ta samu jinkiri wajen wannan farkawar siyasa. Saboda Kudu tana da tazarar ilimi Mai girma akan Arewa, sai 'yan Kudu suka riga 'yan Arewa yin gaba wajen tashi tsaye wajen gwagwarmayar samun 'yanci. Har ila yau, mulki ta kan Sarakuna da ke akwai a Arewa, ya qara tauye ta wajen siyasa da sauran harkokin ci gaba da zamani ya kawo. A haka ake tafiya a shagixe har shekarar 1950.

An yi shawarwari game da sake Sabon Tsarin Mulki a cikin watan Janairun shekarar 1950 a Ibadan. An kuma yi mahawara a kansu a tsofaffin Majalisun Wakilai na Jihohin nan uku, da kuma Majalisar Sarakuna inda aka amince da su xungum.[2] A sabon shirin mulkin, za a kashe Majalisar Dokoki ta Nijeriya, *Legislative Council*. A maimakonta za a sami Majalisar Wakilai ta Nijeriya. Cikinta za a sami wakilan gwamnati shida, da kuma wakilai shida masu wakiltar waxansu harkoki, kamar su Kuza, da su Jiragen Ruwa. Sa'an nan kuma a sami zavavvun Wakilai xari da talatin da shida. Rabinsu kuwa inji Sir Bryan daga Arewa za su zo.[3]

---

1 Sagir Muhammad da Aliyu Isma'ila, *Tarihin Shehu Shagari*. shafi na 50

2 Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 88

3 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 61

Da amincewar Sarkin Ingila, sai aka shiga yin zaven shiga Majalisa, amma sai cikin watan Janairun shekarar 1952 'yan Sabuwar Majalisar suka xauki alqawarin zama 'yan Majalisar. A lokacin ne Sir Bryan ya sami qarin girma ya zama Leftanan Gwamna. A matsayinsa na Babban Razdan na Kano, shi ne kuma ya fi sauran Razdantai girma a Arewa, sai ya zama shugaban Majalisar.[1]

Daga cikin zavavvun 'yan Majalisar Wakilai da aka samu, sai Sir Eric ya karvi aikin kafa Majalisar Zartarwa ta farko domin Jiha, amma sai ya tashi kafin Majalisar ta yi taronta, don haka bai sami damar shugabantar ta ba. Wannan nauyi sai ya faxa kan Sir Bryan. Ita Majalisar Zartarwa, a farkon kafa ta, an yi ta ne da mutane shida daga Majlisar Wakilai da kuma mutum uku daga Majalisar Sarakuna, da kuma ma'aikatan gwamnati, waxanda yawansu ba su fi biyar ba. Waxanda aka zavo daga Majalisar Wakilai su ne:

Muhammadu Walin Barno, daga Majalisar Shehun Barno, wanda ake wa laqabi da *Archdeacon of Borno* da Malam Bello Kano, da Malam Aliyu Makaman Bida. A Majalisar Sarakuna an zavo Sarkin Musulmi Abubakar na uku, da Sarkin Zazzau Ja'afaru, da Aku Uka na Wukari. Akwai Sakatorori uku na ma'aikata, na shari'a, da na kuxi, a cikin wannan Majalisa tare da Razdantai biyu, Rex Niven daga Barno da Conrad Williams daga Zariya.[2]

Malam Aminu Kano bai sami cin zaven shiga Majalisa ba. "Abin baqin ciki kawai shi ne da ba Mallam Aminu Kano a ciki", inji Sir Bryan."Domin kuwa, da dai an sami mutum xaya ko biyu masu cizon NPC a cikin Majalisa, da abin ya fi sha'awa. Kuma da shi Mallam Aminu Kano ya sami shiga, da nauyin kayan zama wakili ya rage masa zafi. Nijeriya ta Arewa, tana buqatar ta tsintsinci duk gwanayen 'ya'yanta, da take iya tsinta. Gwanintar Mallam Aminu Kano, kuwa ba voye take ba."[3]

Shi kuwa Sardauna cewa ya yi ya so Malam Aminu Kano yaci zaven shiga wannan Majalisa. Ya ce, "domin da ya san abin da ake nufi da siyasa ta hanyar aiki, ba siyasar baki ba kurum, wadda za aje Kasuwa a yi ta buxe baki ana hargowa."[4] Ko da yake da wuya a yi siyasa ba tare da hamayya ba. 'yan Siyasan farko sun yi qoqarin siyasa a matsanancin lokaci, sun yi siyasa da gaba, Siyasar NPC da NEPU. Ko da yake babu Siyasar daba a hamayya, a dalilin haka ne Sardauna ya ce, "Ni da abokan aikina da ke zaune a nan kujerar gwamnati ba ma

---

1 Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 88

2 *Ibid*.

3 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na .61-62

4 Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 220

tsoron hamayya - hasali ma dai muna maraba da ita ne."[1] A wannan lokaci da guguwar siyasa ta taso haiqan sai ta murtuke a garin Kaduna.

Kaduna ta taka muhimmiyar rawa wacce kusan babu irinta in banda Bauci da Kano da Zaria da ke Arewa a lokacin da 'yan kishin qasa suka yi gwagwarmayar samun 'yancin Kai da kuma siyasar jam'iyyu ba. Wasu 'yan xaixaikun nazari kamar na su Sklar da Coleman da Dudley sun tofa albarkacin bakinsu a game da gudunmawar da Kaduna ta bayar a lokacin gwagwarmayar 'yan kishin qasa.

Da farko bari mu fara da NPC wacce ta yo asali a watan Satumba na shekarar 1948 a matsayin Jam'iyyar Mutanen Arewa a Yau (JMA) ta Malam D.A Rafin da Dr. R.A.B. Dikko,suka kafa Kaduna ita ce cibiyar wannan jam'iyya. Malam Nuhu Bamalli ya ba da rahoton, cewa an soma batun qirqiro da irin wannan qungiya ce a wajen wani taro na qungiyar Tsoffin Xaliban Kwalejin Kaduna a shekarar 1939. Qungiya ce ta adawa wacce ta boye 'ya'yanta waxanda suke gudanar da harkokinsu ta qarqashin qasa har zuwa shekarar 1949. Wakilai su fiye da xari biyar suka halarci taron qaddamar da qungiyar da ya gudana a Makarantar gwamnati na Kaduna a ranar 26 ga watan Yulin shekarar 1949. Sannan a ranar xaya ga watan Oktoba na shekarar 1951, JMA ta zama jam'iyya. Har ila yau taro na farko na jam'iyyar ya gudana ne a Kaduna a ranar 5 ga watan Yulin shekarar 1952. Yana da kyau a lura cewa an gudanar da taro na farko ne a Otel xin Mr. Green da ke a kusa da titin Kano daura da titin Ahmadu Bello a Sabon Garin Doka. Sannan kuma a kusan lokaci guda ne aka kafa wasu jam'iyyun da dama a sauran garuruwan yankin Arewa waxannan jam'iyyu kuwa su ne:

NEPU a Kano a shekarar 1949, da Qawancen Shiyyar Tsakiya (M21) a shekarar 1951, da Haxaxxiyar qungiyar Tsakiya (UMBC Jos) a shekarar 1954, da Qungiyar Matasan Borno (B/M Maiduguri) a shekarar 1954, da I TP ta Ilorin a shekarar 1954. Kuma wani abu da za a lura da shi a nan shi ne NPC ba ta kafa wata sakatariya ba daga shekarar 1951 zuwa 1954 kamar yadda sauran jam'iyyun irin su NCNC ko A.G. suka yi ba. A dukkan tsawon wannan lokaci waxanda ke mamaye da sakatariyar shalkwatar jam'iyyar su ne babban Sakataren shirye-shirye Malam Nuhu Bamalli da Sakataren Mulki Malam Garba Abiya. Sai dai a shekarar 1954 lokacin da aka naxa Sir Ahmadu Bello a matsayin sabon Shugaba na Qasa baki xaya, aka mayar da shalkwatar jam'iyyar NPC zuwa Kaduna.[2]

Kuma daga shekarar 1955 sakatariyar ta ci gaba da faxaxa qarqashin Dr. R.A.B Dikko, da Malam Rafih, da M. Raji Abdullah, da Malam Yusuf Dantsoho da Malam Muhammadu King. Kuma daga wannan shekara ne Kaduna ta zama muhimmiyar cibiya ta harkokin siyasa a yankin Arewa, ba ga NPC kawai ba, har ma ga dukkan sauran jam'iyyun siyasa cikinsu har da NEPU.

---

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 221

[2] E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation in Northern Nigeria*, shafi na 496

Kaduna ta zama babban sansanin NEPU a shekarar 1950. Kuma yana da muhimmanci a sani a nan cewa jam'iyyun da ke adaw a da NPC a zavuvvukan shekarar 1951 sun samu nasara a mazavu takwas cikin guda guda goma sha-tara da aka kira. NPC ta yi yaqi a matsayinta ta jam'iyya amma ba qungiya ta idon gari ba. Sannan a zaven shekarar 1956 Kaduna na xaya daga cikin mazavun da NEPU ta yi nasara, sauran wuraren kuma su ne Zariya da Jos da Qauran Namoda. Sauran jam'iyyun sun yi nasara ne sakamakon qawance da jam'iyya A.G. ta yi da ta ITP a Ilori da Offa, da kuma qawancen da BYM ta yi da NEPU a Yerwa ta Arewa da Kudu.

A watan Nuwamba na shekarar 1957 lokacin da gwamnatin yankin Arewa ta kafa Majalisun Qananan Hukumomi huxu a babban birnin Kaduna, sakamakon zaven da aka gudanar na zuwa majalisun duk iri guda ne. A Kaduna ta tsakiya wacce ta haxa da Sabon Gari, da sabon rukunin gidaje da qauyen Kabala da ke da wakilai talatin da uku, NEPU/NCNC sun ci kujeru ashirin da xaya, sai AG/UMBC kujeru goma sha-biyu, sai NPC wacce ba ta samu kujera ko guda xaya ba. A Kaduna ta Yamma wacce ta qunshi Tudun-Wada wadda kuma ke da wakilai talatin, qawancen NEPU-NCNC sun samu kujeru goma sha-shida, sai NPC mai kujeru goma sha-huxu, sai qungiyar Tsoffin Ma'aikata da ta samu kujera xaya tal. A Kaduna ta Kudu da ta haxa da Maqera da Kakuri Hausa da Kakuri Gwari da Barnawa wadda kuma ke da wakilai talatin, NPC ta cinye kujeru ashirin, sai NEPU-NCNC wadda ta samu kujeru goma. A Kaduna ta Arewa kuwa wacce ta haxa da qauyukan Kawo da Unguwar Shanu kuma ke da wakilai talatin da uku, NEPU da NCNC na da kujeru 21, sai NPC mai kujeru 12.[1]

A babban zaven shekarar 1956 Malam Bala Keffi na jam'iyyar NEPU ya doke xan takaran jam'iyyar NPC Malam Haruna Xan Birni zuwa Majalisar Dokoki ta Arewa. Sai dai sakamakon muhimmancin da gwamantin yankin Arewa ta NPC ta xora akan Kaduna sun dage a shekarar 1960 domin sun cinye zavuvvukan Kaduna. A zaben shekarar 1961, NPC ta doke NEPU da qyar da jivin goshi inda daga nan ta tsaya ta riqe Kaduna katakam ta yadda ko a zaven Tarayya da aka yi a shekarar 1964 xan takaranta ne ya samu rinjaye ba qarami ba. Ita kuma NEPU ta ci gaba a tsawon Jamhuriya ta Farko, da taka muhimmiyar rawa a birane, (Musamman waxanda aka kafa a zamanin Mulkin Mallaka) fiye da birane irin su Kaduna da Minna da Kafanchan da Qauran Namoda da Gusau da Nguru da kuma mai yiwuwa Jos. A dukkan waxannan garuruwa da ke da reliwai, NEPU ta samu nasara. Bugu da qari jam'iyyar ba qaramar mamaya ta yi ba a tsoffin biranen Kano da Zariya.[2]

---

[1] E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation in Northern Nigeria*, shafi na 498

[2] *Ibid.*

Magoya bayan jam'iyyar NEPU a Kaduna kamar yadda na sauran wurare suke, yawancinsu talakawa ne da suka haxa da qananan 'yan tireda, da masu sana'o'in hannu, da makanikai, da teloli, da leburori da ke aiki a hukumomin gwamnati da ma'aikatan kamfanoni da masana'antu. Siyasar aqida da NEPU ta nuna a watan Oktoba na shekarar 1952 ya sanya jam'iyyar ta tserewa sauran jam'iyyun wajen jan hankalin talakawa.

Har ila yau nasarar da NEPU da sauran jam'iyyu suka samu a biranen Arewa kamar irin su Kaduna na nuna raunin da jam'iyyar NPC ke da shi a matsayinta na jam'iyya. Saboda a nan ne aka gudunar da zavuvvuka akan ginshikin 'yancin mai biyan haraji.

Misali tun shekarar 1951 da NEPU ta miqe tsaye wajen yaqin neman zave a Arewacin Zariya, inda ta dage wajen sukar mulkin Sarakuna; kuma a wannan lokaci, En'e ta Zariya ta dingi, kamawa tana xaure 'ya'yan jam'iyyar saboda gudanar da tarurruka daban-daban da aka haramta kowasu take-take qarqashin sashe na 37 na Dokar En'e da Majalisar Dokoki ke da iko da ita. Ayar tambaya a nan ita ce:

> *Shin tasowar da Jam'iyyun Siyasa suka yi bayan shekarar 1945 ya kawo muhimman sauye-sauye ga (zamantakewa da tattalin arziqi) na mutanen Kaduna kuwa? Domin amsa wannan tambaya, yana da kyau. Mutum ya ayyana a cikin zuciyarsa cewa ci gaban siyasa yanayin ci gaban jam'iyyun siyasa a Kaduna abu ne mai sarqaqiyar gaske. A tsawon zamanin da aka yi ana siyasa har zuwa shekarar 1960, siyasa ce da za ka ga NPC ke da ikon gwamnatin yanki, sai NEPU da ke da iko da Qaramar Hukumar Kaduna, sai Qauyukan Hausawa da na Gbagyi da jama'ar 'yan qasa ke iko da su. Wannan ya haifar da manya-manyan matsaloli na tsare-tsare da gudanar da mulki kamar yadda ya kamata, wanda daga bisani ya shafi buqatun al'umomi da ke birane. Sakamakon wannan savani da rikice-rikice da hamayya da gasa, zavavvun shugabanin Qaramar Hukuma sun gaza xaukaka ci gaban tattalin arziqin yankunan karkara, da gudanar da Mulki kamar yadda ya kamata, ko baiwa maraxa kunya a game da amincewa da kuma biyayyar da jama'a ke yi masu.*
>
> *Wannan babi ya duba dangantaka tsakanin zamantakewa da siyasa, da sauye-sauye na siyasa da suka auku bayan shekarar 1945 da ci gaba da aka yi ta samu akai-akai na ci gaban birane a Kaduna a shekarar 1945 – 1960. Har ila yau babin ya nuna cewa Kaduna har zuwa shekarar 1956 birni ne na Soja, da ma'aikatan reliwai, da jami'an Mulki da Akawu-Akawu. Har ila yau cibiya ce ta manyan makarantu da ke Arewacin Nijeriya. Sauran waxanda ke kwarara*

zuwa Kaduna su ne ko dai 'yan tireda ko masu sana'o'in hannu da ke biyan bukatin ma'aikatan da aka ambata a sama. Sai dai daga shekarar 1956 Kaduna ta zama babbar cibiyar masana'antu da harkar kasuwanci ta yankin Arewa.[1]

Tasirin waxannan bambance-bambance na jam'iyyun siyasa a ci gaban al'ummar da ke birnin Kaduna na xaya daga cikin dalilan da suka zama tarnaqun hana ci gaba saboda mummunar gaba da hamayya da ke tsakanin NPC da NEPU. A nan sai a ba da taqaitaccen tarihin yadda aka kafa manyan jam'iyyun NPC da NEPU a Arewa. A kuma nan gaba ayi bayanin yadda siyasar gaba da tsageranci ta hudo kai a Arewa.

Dalilan Kafa NPC

Mai girma Alhaji Nuhu Bamalli, M.H.R., ya bayyana yadda aka kafa mashahuriyar Jam'iyyar Mutanen Arewa, wato NPC. Ga Bayaninsa:

A taron Qungiyar Tsofaffin Xaliban Kwalejin Kaduna da aka yi a shekarar shekarar 1931, a harabar Kwalejin Kaduna ne aka haifi jam'iyyar NPC. A wannan taro aka dasa ra'ayin samar da haxaxxiyar Arewa kuma taron ya samu wakilcin dukkan sassan Arewa. M. Alhaji Dogon Daji, shi ne wanda ya shugabanci wannan taro. Tun daga wannan rana ne muhimmancin samar da Arewa qasa xaya da tsoron Mallakar Kudu ke zukatan duka 'yan Arewa masu ilimi. Amma da jin labarin vullowar wannan qungiyar sai hukuma ta tsorata ta kuma hassala hukumar En'e da ta yi kaffa-kaffa da wannan Qungiyar Tsofaffin Xaliban Qwaleji wato College Old Boys Association (COBA). A dalilin haka ne sai aka xauki matakin da za a daqile wannan qungiya.

'Yan tsageran qungiyar sai suka fara aikin yaxa qungiyarsu tuquru kuma a cikin sirri, suna kiran 'yan Kwaleji ga muhimmancin kafa haxaxxiyar Arewa. Saboda haka sai nan da nan aka riqa samun kafuwar zaurukan tattaunawa wato (Discussion Circles), a manyan garuruwan Arewa. Abubuwan da ke cimma 'yan Kwalejin tuwo a qwarya su ne, yadda za su (1) su darkake Mulkin Mallaka da (2) su kare Arewa daga mallakar Kudu. Akwai wani dalili da bai faxaba wanda shi ne su rusa muxlaqin mulkin Sarakuna, wanda yana daga

[1] E.O. Oyedele, *Colonial Urbanisation in Northern Nigeria*, shafi na 501

cikin babban burin 'yan wannan qungiya. Wannan buri ne ya dasa qwayar hamayya da Sarakuna a zukatan masu ilimin zamani a Arewa.

Musabbabin dalilin da yasa 'yan Arewa masu ilimin zamani ke xaukar wannan gwagwarmaya saboda duk da qarin masu ilimi da ake samu duk kuma da qwarewarsu amma abin takaici sai suka ce an maida su fifa-iya-koma-baya, a harkokin ayyukan En'e. A dalilin haka ne sai aka shiga zaman doya da manja tsakanin 'yan bokon Arewa da shugabannin En'e da magoya bayansu Turawan Mulki. Wasu daga cikin 'yan tsageran wannan qungiya sai suka fanxare suka shiga cikin jam'iyyun Kudu musamman NCNC da *Nigerian Youth Movement* (NYM). Waxanda su ma sun zaqe wajen faxa da Sarakunan Arewa.

Amma waxanda basu fanxare ba, sai suka ci gaba da ayyukansu a voye, suna qoqarin jawo hankalin matasa ta kafa Zaurukan Tattaunawa a cibiyoyi da dama a garuruwan Arewa. Turawan mulki ne suka hura wutar qiyayya da hamayya a tsakanin Sarakuna da masu ilimin zamani. Saboda idan aka samu haxin kai a tsakaninsu, to, suna iya juyawa Turawa baya, su kore su a wannan qasa mai albarka kamar yadda 'yan Kudu ke fafitikar ganin guguwar yaqin neman 'yanci ta turnuqe a Arewa. Amma idan aka haddasa gaba a tsakaninsu ta *Divide et impera*, Turawa za su daxe suna jan zarensu a Nijeriya. Saboda haka sai aka cunkusawa matasa hamayya da adawa da Sarakunan su ba kishin Arewa ba.

Ita wannan da'irar tattaunawa ta Zariya, sai ta zama qungiyar Abokai ta Zariya, wato Zariya *Friendly society* daga bisani kuma ta zama qungiyar ci gaban Zazzau ko Zaria *Provincial Progressive Union* da Sauransu.

A watan Disamba na shekara 1949 ne aka yi wani babban taro a Kaduna don bukin kafa wata sabuwar qungiya mai suna jam'iyyar Mutanen Arewa ko *Northern Peoples Congress* (NPC) da Turanci. Ita wannan Jam'iyya sai ta taso da sassauci ga Sarakuna da kuma kyawawan manufofi. Jam'iyyar kuma ta xauki alqawurran aiwatar da ayyuka masu amfani wajen ciyar da Jihar Arewa gaba.

A wannan lokaci Turawan Mulki ba sa son ganin Arewa ta farka a siyasa saboda haka sai suka riqa xari-xari da wannan jam'iyya saboda tsoron kada ta kifar da Mulkin Mallaka. Amma sai Turawa suka yi kutingwilar hana 'yan Arewa masu ilimin boko samun ayyuka a qarqashin En'e domin sun ba Sarakuna shawarwari kada su amince da su.

Malam Shehu Shagari ya ce a dalilin haka ne sai masu ilimi da yawa 'yan Arewa waxanda ba su da wuraren aiki suka shiga qungiyoyin siyasa a kudancin Nijeriya musamman jam'iyyar NCNC. Xaya daga cikin irin waxannan mutanen Arewa, shi ne marigayi Malam Sa'adu Zungur, wanda aka tura makarantar Yaba

Higher College, domin ya karanta hanyoyin harhaxa magunguna, amma sai ya afka siyasa, a dalilin haka suka koro shi daga makarantar, ya dawo Arewa.[1]

Malam Sa'adu Zungur ne ya shigo da siyasar NCNC wadda bata dace da Arewa ba wadda kuma itace ta hura ruhin jam'iyyar NEPU. A Kudu jam'iyyun adawa da NPC su ne jam'iyyar NCNC da jam'iyyar AG. A Arewa kuma, itace jam'iyyar NEPU. A dalilin haka ne sai NPC ta fuskanci adawa a ciki da wajen Arewa. Saboda haka sai Arewa ta taso babu haxin kan jam'iyyun siyasa kamar na Kudu. A dalilin haka ne ma siyasar tsageranci ta hudo kai a Arewa, wanda har yanzu babu haxin kai a harkar siyasa. Ko da yake akwai 'yan Arewa masu ilimi waxanda suka yi qoqarin kashe harshen wutar siyasar tsageranci amma basu da yawa.

A wajen taron NPC da aka yi a Jos, a cikin shekara ta 1950, Malam Shehu Shagari ne ya wakilci Sakkwato, kuma a jawabin da ya yi ga wannan taro, ya gabatar da shawarwari waxanda yake yi wa wakilci da suka buqaci idan an zo zave, ya kamata a tantance domin kada a zavi tsagera waxanda zukatun Sarakuna ke cike da fushinsu, saboda zaven tsagera na iya hassala Sarakuna su yi xammarar jihadi da wannan jaririyar jam'iyya, haka kuma ko da Turawa ba su fito fili sun nuna ba, to, babu shakka za su xauki wannan jam'iyya a matsayin abokiyar gaba. Wannan magana da Shehu Shagari ya yi, da yawa daga cikin tsagera ba su ji daxinta ba. A nan ne Shehu Shagari yaci karo da fushin Sa'adu Zungur, wanda ya bayyana rashin jin daxinsa, har ta kai shi ga ya fito fili, ya ce, "Tuni Sakkwato ta daina aiko da umurni."[2]

Malam Sa'adu Zungur shi ne xan Arewa na farko da ya fara samun sikolaship na qarin ilimi a wajen Jihar Arewa. gwamnatin Mulkin Mallaka ce ta bashi tallafin kuxi fam goma sha-shida domin ya qaro ilimi a kwalejin Yaba da ke Ikko. A wannan shirin Sa'adu zai xauki tsawon shekara guda a wannan kwaleji inda zai karanci fannonin *Biology* da *Chemistry*. Saboda haka sai a watan Janairu na shekarar 1934, Sa'adu ya bar kwalejin Katsina zuwa kwalejin Yaba, a matsayin xan Arewa na farko wanda ya fara samun irin wannan tallafi.[3]

Amma da zuwansa Ikko sai ya yi watsi da harkar ilimi ya shiga cikin badaqqalar siyasa. A dalilin haka ne sai aka koroshi ya dawo Arewa.[4] Saboda haka sai ya gaza wajen jagoranci 'yan Arewa a fannin ilimi. Ko da yake shi ne limamin siyasa a Arewa amma siyasar da ya shigo da ita Arewa samfurinta NCNC cewadda take siyasar tsageranci ce saboda a zamansa a Ikko Sa'adu ya

---

1 Sagir Muhammad Da Aliyu Ismaila, *Tarihin Shehu Shagari*, shafi na 61

2 *Ibid*.. shafi na . 63-64

3 A.M Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na 16

4 Nuhu Bamalli, *How the NPC was founded*, Jaridar NC, 15/5/ shafi na 4

jarabtu da son Dr. Nnamdi Azikiwe da jam'iyyarsa ta NCNC. Saboda haka sai ya dasa samfurin siyasarsa a Arewa takan dalibinsa Malam Aminu Kano shugaban NEPU, wadda itace 'yar adawar jam'iyyar NPC. Tun daga wancan lokaci har yanzu qungiyoyin siyasa a Arewa suka zama masu tufka da warwara a harkokin siyasa, ba irin jam'iyyun Kudu ba masu manufa da haxin kai ba.

Ko da yake qungiyar COBA wadda ke da manufar kifar da mulkin Sarakuna ce ta haifar da jam'iyyar NPC amma sai wannan jam'iyya ta sassauta adawarta da Sarakuna. A dalilin haka sai ta zama jam'iyya mai kyawa wan alqawura.

Alqawuran NPC

Jam'iyyar NPC ta yi babban taro a filin makarantar gwamnati ta Kaduna. 'Yan qungiya da shugabanni sun hallara. Manyan shugabannin qungiyar sun haxa da Minista Aliyu Sardauna, da Minista Abubakar Tafawa, da minista Muhammadu Ribaxu, da Minista Makaman Bida, da Minista Abba Habib, da Muhammadu Inuwa Wada. A wannan taro ne Sardauna ya bayyana cewa NPC ta yi niyyar cika alqawura goma sha-uku da ta yi in an zavi ya'yanta a zaven da za a yi:

(1) Faxin gaskiya da, aikata gaskiya; (2) Tsai da shari'ar gaskiya; (3) Yaqi da zalunci, jahilci da lalaci. Za mu kashe baqaqen al'adu, mu raya masu kyau; (4) Kafa makarantu ko'ina cikin dukkan manyan garuruwa da manyan qauyuka. Bayar da ilimi mai zurfi ga maza da mata, yara da manya. Taimakon kafa makarantun addini da gyaransu. Za mu qara yawan makarantun sana'a, Arewa za ta sami makanikai da kafintoci da sauran masu sana'a, ba da mun nemo su daga wata qasa ba; (5) Samo hanyoyi yadda manoma za su sami albarkar abubuwan da su ke shukawa da yadda za su sayar da amfaninsu da daraja. Mun shirya gwamnati za ta ajiye waxansu kuxi musamman, waxanda za a riqa ba manoma rance, don faxaxa gonakinsu da yadda kowane manomi zai sami garma da shanun noma, da kuma 'yan dabbobi nasa. Muna shirya yadda manoma za su sami rance daga gwamnati lokacin tsananni; (6) Za mu kakkafa gidajen magani a ko ina da ina, tun ma ba cikin qasa, yadda dukkan jama'a za su sami zarafin sarrafad da kayayyakinsu ba da matsanancin wahala ba; (7) Za mu buxe hanyoyi cikin qasa, yadda dukkan jama'a za su sami zarafin sarrafad da kayayyakinsu, ba da matsanancin wahala ba. (8) Niyyarmu mu taimaki 'yan kasuwa da fahintar da su hanyoyi iri-iri, yadda su da kansu za su iya yin odar kayayyaki daga sauran qasashen duniya, da yadda za su gane amfanin haxa kansu don kafa kamfani; (9) Za mu ci gaba da aikawa da xalibai maza da mata zuwa waxansu qasashe saboda qaro ilimi. Za mu aika da su Ingila, Masar, Sudan, Pakistan, Indiya da ko'ina inda za a qaru da ilimi; (10) Za mu qarfafa dukkan majalisun Sarakuna da na Hakimai da na Dagatai, yadda jama'a za su sami zarafin kawo koke-kokensu, su kuma faxi kowane irin ra'ayi nasu, ba da wata fargaba ba; (11) gwamnatinmu ta shirya yadda dukkan ma'aikata da sauran jama'a za su sami rance daga kuxin gwamnati don

gina gidaje masu kyau; (12) gwamnati ta yi babban tanadi game da ruwan famfo a birane da qauyuka. Niyyarmu kowane gari da kowane qauye su sami ruwan sha mai lafiya, mai kyau. (13) Niyyar wannan Jam'iyya ne nan da nan ta kawo qaruwar ci gaba da arziqin mutanen wannan jiha, yadda kowane mutum da mace, yaro da yarinya, na wannan jiha za su ci amfanin qasarsu, su tsere wa talauci, huntanci da yunwa.[1]

Ko da yake wannan jam'iyya ta yi qoqari wajen cika wasu daga cikin waxannan alqawura amma har yanzu Arewa na buqatar ci kasa waxannan alqawurra saboda muhimmancin su a wannan zamani a yau! Ita wannan jam'iyya ta Sarakuna da attajirai cewadda kuma ke samun goyon bayan Turawan Mulki a zahiri. Sardauna wanda ya jagoranci wannan jam'iyya sai ya yi kira ga jama'ar Arewa a yaqin neman goyon bayansu ga jam'iyyarsa.

Sardauna ya yi Kira ga 'Yan Arewa

Firimiyan Jihar Arewa, Mai girma Sardauna Ahmadu, ya yi jawabi a rediyon Nijeriya, yana kiran 'yan Arewa su zavi 'yan NPC su wakilce su a Majalisar Nijeriya. Ya ce, "Mu Jam'iyar NPC mun tabbata babu wanda ya san Arewa fiye da 'yan Arewa, kuma mun tabbata duk irin wahalce-wahalcemmu na Jihar Arewa, babu wanda zai iya gyara mana su, in ba mu da kammu ba, mutanen Arewa.

Haka Kuma Firimiya ya ce, "Mutanen da za ku zava, ya kamata su zama amintattu, mutane irin waxanda don kuxi ko don kwaxayin girma, ba za su sayad da Arewa da jama'arta ga mutanen Kudu ba. Babu wanda ya yi mamakin abotar NCNC da NEPU, domin duka jirgi xaya ya xauko su. A wannan jawabi ne ya ce:

> *Assalamu Alaikum. Na yi murna da yi muku wannan magana yau, bisa kan sha'anin jam'iyyarmu, wato NPC, Jam'iyyar Mutanen Arewa. Yanzu zan gaya muku manufar wannan jam'iyya tamu, game da zaven Wakilai da a ke cikin yi.*
>
> *Duk daga cikin jam'iyyoyi na mulki na Nijeriya, Jam'iyyar NPC ce kawai wadda ba ta tava sake manufarta ba. Tana tsaye kan niyyarta ta farko. Xaya daga cikin niyyar jam'iyyarmu, shi ne a kan al'amura na gida, kowace jiha ta lura da kanta, amma a bisa al'amura waxanda suka shafi qasa duka, muna so jihohi su haxu, su yi shawara gaba xaya.*
>
> *NPC ta tabbata a bisa kan wannan ra'ayi nata ne kawai mutanen Arewa, qabilu daban-daban, za su sami sukunin haxa kansu su zama uwa xaya uba xaya. Mu Jam'iyyar NPC, mun tabbata babu wanda ya san Arewa fiye da 'yan Arewa, kuma mun tabbata duk irin*

[1] GTK, 22/9/1954, shafi na 7

wahalce-wahalcemmu na Jihar Arewa, babu wanda zai iya gyara mana su, im ba mu da kammu ba, mutanen Arewa.

Jam'iyyar NPC ba ta tava mafarkin tsalma baki cikin al'amuran gida na sauran jihohi ba, haka kuma Jam'iyyar NPC ta mutanen Arewa ba za ta yarda sauran jihohi su yi mata kankamba cikin al'amuranta na gida ba. Jam'iyyar NPC ta mutanen Arewa ta himmatu bisa yin waxannan ayyuka domin rayuwar Arewa.

Da farko niyyarmu mu tsare mutuncin jama'ar Arewa, yadda ba za su wulakanta ba, mu ba kowa zarafin bin irin addinin da ya ga dama, mu qarfafa xabi'o'immu da al'adunmu masu kyau, mu yaxa ilimi, kowa da kowa, mu buxe makarantu iri-iri na addini da na sana'a ko ina cikin qasa, kuma mu aika da yarammu maza da mata zuwa waxansu qasashe, don samun ilimi mai zurfi.

Duk wuraren ayyukanmu mutanenmu za mu sa. Babban abin da Jam'iyyar NPC ta mutanen Arewa ta sa gaba kuma, shi ne qarfafa shari'ar gaskiya, yadda alqalai da mahukunta za su yi shari'a bisa gaskiya da adalci, ba da tsoro ba, ko kuma son zuciya. Niyyarmu jama'ar Arewa su zauna lafiya cikin kwanciyar rai.

Ni na tabbata jama'ar Arewa mutane ne masu hankali, waxanda za su iya bambancewa tsakanin mutanen kirki, waxaanda su ke qaunarsu, su ke qoqarin kawo musu alheri, da miyagun mutane, waxanda su niyyarsu kawai su sayad da.[1] *An kafa jam'iyyar NEPU bisa wasu dalilai tana kuma da manufofinta, a matsayinta na qungiyar siyasa, wadda ta farkar da talakawan Arewa a kan su tashi su yaqi zalunci da danniya.*

Dalilan Kafa NEPU

A taron Tsarin Mulki da aka yi a Ibadan a watan Janairu na shekarar 1950, Tsarin Mulki na MacPherson ya sami kakkausar suka ainun, wani hali da ya kawo barazana ga haxin kan Nijeriya. Wakilan Jihar Arewa a wannan taro, akasarin su Sarakuna ne don haka ba su nuna wargi ba sai da suka tsaya tsayin daka wajen ganin wajen ganin sun kai nasara akan abin da suka tsaya akai, har barazanar yanke wa daga Nijeriya suka yi, wannan al'amari ya tada hankali a kan haxin kan Nijeriya.

A wannan lokaci ne wasu matasan Nijeriya suka yi hovvasa wajen ba da gudunmawarsu ta kafa jam'iyyar siyasa. Malam Sa'adu Zungur, Sakataren NCNC na qasa, da Malam Aminu Kano, malami a Kwalejin Malamai da ke Maru suka

[1] GTK, 22/12/1954 shafi na 6

kafa qungiya mai suna *Northern Element Progressive Unioun* (NEPU), a ran talata 8 ga Agustan shekarar 1950, a cikin birnin Kano. A wannan rana ce mashahuran 'yan qungiyar guda takwas suka hallara: Bello Ijumu, da Abba Maikwaru, da Mudi Sipikin da Magaji Xambatta, da Baballiya Manaja, da Musa Kalla, da Abdulqadir Xanjaji, da Garba Bida.[1]

Waxannan mutane takwas ne suka kafa NEPU, a ranar takwas ga watan takwas xin shekarar 1950 da qarfe takwas na safe (8/8/1950 da 8am). An kafa wannan jam'iyya ne a qarqashin shugabancin M. Abba Mai Kwaru da M. Bello Ijumu, a matsayin Sakatare.[2]

Saboda haka sai wannan jam'iyya ta 'yan Arewa masu kishin qasa ta taso da kishin qasa. A dalilin mummunar kusan da suke samu da kuma zargin rashin kishin Addinin musulunci da ake masu, daga Turawan Mulki takan Sarakuna, sai Malam Aminu Kano da sauran Shugabannin Jam'iyyar suka fito wurjanjan suna amfani da zurfin iliminsu na Addinin musulunci suna qalubalantar Turawan Mulki da Sarakuna akan zaluntan talakawa da suke yi tare da wasu fassara sharuxxan musulunci domin biyan buqatunsu.

A dalilin haka ne ma Jam'iyyar NEPU ta kafa ofishin mai ba da shawara ta qasa a kan harkokin Addinin musulunci. Malam Lawan Danbazau da Malam Aminu Kano sun sami yabo matuqa daga matasa da samarin Arewa saboda yadda suka yi amfani da iliminsu na Alqur'ani da Hadisi wajen kare duk zargin da ake wa qungiyar NEPU.[3]

Manufofin NEPU

Hajiya Gambo sawaba mashahuriyar 'yar NEPU ta bayyana cewa Jam'iyyar NEPU nada waxannan manufofi waxanda kuma ta yi amanna a kan su:

i. Sanadiyyar tavarvArewar tsarin rayuwar al'umma a halin yanzu a nan Jihar Arewa Saboda gudanar da tsarin "N.A" na nagada ne da ke gallazawa jama'a.
ii. Saboda kasancewar irin wannan tsarin mulki na nagada ne da aka kafa kuma gwamnatin Turawan Mallaka na Birtaniya ta goya wa baya, to, a

---

[1] Alkasim Abba (ed). *The Politics of Malam Aminu Kano Documents from the Independence struggle 1950-1960*, Vanguard Printers and publishers Ltd Kaduna (2006), shafi na .11-12

[2] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba: Kallabi Tsakanin Rauwuna*, shafi na 55

[3] Alkasim Abba (ed). *The Politics of Malam Aminu Kano Documents from the Independence struggle 1950-1960*, Vanguard Printers and publishers Ltd Kaduna (2006), shafi na . 12

yau a cikin al'ummarmu akwai savanin ra'ayi da ya haddasa gwagwarmaya tsakanin masu hannu da shuni da kuma talakawa.

iii. Za a iya kawar da wannan qiyayya ta hanyar 'yanto talakawa daga cikin qangin mallaka na waxa nnan tsirarun masu hannu da shuni ta hanyar sarrafa al'umma bisa kan tsarin Dimukuraxiyya, kazalika sanya ragamar jansu ga hannayen talakawa, wato Dodon da ake yi `wa bauta.

iv. Qwato wannan 'yanci ya kasance da qarfin tuwo da gumin su Talakawan da kansu.

v. A halin yanzu saboda kasancewar gwamnati tare da sojojin qasa saboda tsare martabobin 'yan tsiraru masu hannu da shuni, dole ne talakawa su haxe kansu ta fuskar siyasa domin karve ragamar gudanar da harkokin gwamnati da sojoji, yadda za a tunvuke harsashin zalunci da kama-karya, a kafa wani sabon tsari na qwato 'yanci da tabbatar da adalci, a yi watsi da martabobin 'yan tsiraru tare da tsarin gudanar da harkokinsu.

vi. Maqasudin kasancewar jam'iyyun siyasa shi ne bayyana ra'ayin azuzuwan da ke cikin al'umma amma za ka ga cewar duk abin da ya shafi rayuwar talakawa ba ya yin kunnuwan doki da na sauran azuzuwa da suka qumshi babban ajin masu hannu da shuni, Farar Fata ko Baqar Fata zaka ga duk jam'iyyar da ke yunqurin qwato 'yancin talakawa tana sa'insa kuma bata jituwa da jam'iyyar marasa adalci, azzalumai.

vii. Saboda haka ita Jam'iyyar NEPU a nan Jihar Arewa a matsayinta na Jam'iyya xaya tilo ta talakawa ta tsunduma cikin fagen siyasa tare da niyyar rage munafukai da 'yan Tawayen qasarmu; sabili da haka take kira ga dukkanin 'ya 'yayen wannan Jihar mazansu da matansu da suka hallara qarqashin tutarmu har tura ta kai bango (qarshe), da su ja xamara domin kawo qarshen wannan mugun tsari na mulkin al'umma wanda ya haramta masu cin moriyar guminsu.[1]

Alqawarin NEPU

Jam'iyyar Neman Sawaba, wadda da Turanci a ke kira *Northern Elements Progressive Union* (NEPU), wato Jam'iyyar Talakawa da Masoyansu, za ta shiga wannan zaven zuwa Babbar Majalisar Mulkin Nijeriya da tsarkakkiyar zuciya game da tawali'u zuwa ga Ubangiji, da niyyar qwato wa al'ummar Arewa musamman, da na Nijeriya, baki xaya, haqqoqinsu don qasa baki xaya ta zama rayayya, qaqqarfa, Mai girma da martab a a idon duniya. Ba tsimi, ba dabara, face daga Allah Mai girma da Xaukaka:

[1] Ahmad Abdulqadir, Gambo Sawaba: *Kallabi Tsakanin Rawuna,* shafi na . 127 and 129

1. Gabatar da hanyar kiyaye haqqoqin jama'a, (*Fundamental Human Rights*) wato kiyaye rayukansu, mutuncinsu, dukiyarsu, lafiyarsu da addininsu. Ganin irin yadda darajar talaka ta zama a bar ja a qasa, da ganin yadda a ke tursasa haqqin marar qarfi shi ya sanya NEPU ta fara yaqi ta nan, domin idan ba martabar mutum ce ta tabbata ba, komai irin dukiyarsa ba zai wuce wulaqanci ba. Mutum shi ne wani abu, domin kowa yana da baiwa irin tasa. Ba wanda ya fi wani sai wanda ya fi tsoron Allah.
2. Qarfafa gama kan Nijeriya da niyyar samun qaqqarfar qasa, Strong Federal State, inda kowa zai wala, ya zama ba abin tsangwama ba, ko daga wace jiha yake. NEPU ba ta so mutum ya je wata jiha ya riqa jin shi ba komai ba ne, ko ya riqa jin shi abin tsangwama ne. Ko da yake muna zaune jiha jiha, duk da haka Nijeriya qasa xaya ce, wadda kowa zai yi alfahari da ita.
3. Kyautata al'amuran shari'a, ta yadda za a tsara hanyar tabbatar da adalci da kawar da wulaqancin da maqaraya maza da mata ke sha, balle in ba su da abin hannu. Shirya masaukin maqaraya da kula da su. Tsara hanyar jin qarar mutum don a huta da komo gobe. Duba al'amuran aikin 'yan Doka da danganansa da alqalai da niyyar kawar da zaluncin da ke haddasuwa ta wannan fuska. Yaqi a kan gyara maganar afil, appeal, daga ko wace kotu har zuwa qarshen wurin qara a kan ko wane laifin da ya xaure mutum wata uku ko fi.
4. Tabbatar da sabon tsarin aikin gidan gona, ta yadda za a sami isasshen abinci ga kowa a ko wace rana, saboda kawad da yunwar da ta rarrafo qasar nan a yanzu har ta kai a yau mutane, balle na qauye, cikin muna shakka su ke zaune don qarancin abinci da ruwan sha. Shirya wa manoma hanyar gudunmawar kuxi daga gwamnati, don su himmatu wajen shuka irin abin da zai amfani qasa da kuma yadda abin da ke fita zai yi tsada. Irin wannan gudunmawa, *subsidy*, za a iya xibanta daga ajiyayyun kuxin da aka samu daga hannun manoma, wanda yanzu sun taru an qi yin komai da su.
5. Binciken dokokin aikin daji da aikin fata, saboda gyara wuraren da ayautar da su yake damun talakawa. Hana aikin tilas na al'ada da karvar gonakin talakawa. Tsara aikin kurkukun En'e ta yadda xaurarru za su dena gamo da wahalce-wahalcen da ba sa kan qa'ida ko oda. Hana sa qananan yara biyan haraji.
6. Bincike da sake shirin albashin ma'aikata (balle na En'e da leburori) yad da albashi zai dace da tsadar abubuwa. Shirin kula da su ta wajen ciwo, ko neman taimako da kuma lura da 'ya 'yayensu.
7. Qallafa wa gwamnati ta buxe sabuwar hanyar lura da marasa lafiya sosai. Qara yawan asibitoci da wuraren shan magani, hana cuta yaxuwa da kashe

ta baki xaya, gina asibitin jarirai da makarantun koyon raino, (Domestic Science Centres) xakunan taro da nishaxi ko hira, wasannin yara da shan iskar manya.

8. Kafa doka a kan maganar ciniki da danganensa da baqi, ta yadda za a sa dukan baqi masu kafa kamfani su gama kai da 'yan qasa kafin zamansu ya tabbata, domin a kawar da zaluncin da ke haddasuwa yanzu. Shirya yadda za a kafa na'ura mai yin abubuwan da qasa ke buqata, wato kamar su sabulu, mai, takalmi, tufa, qananan abin hawa, abinci, kayan gini, lantarki, da sauransu.
9. Binciken yadda manyan kogunanmu da taffukamu za su zama masu amfani ga talakawa ta wajen aikin lambu da shuke-shuken rani. Yin haka shi zai kawar da zaman banza, wanda yake kawo ciwo, rashin niyya da kuzari da rashin ci gaba. Yin haka ne zai sa talaka ya sami abubuwan da rai ke buqata ya zauna hani'an, ya sami damar ilimi da bautar Ubangiji.
10. Tsara sha'anin ilimi da gama kan malaman makarantar Nijeriya da gyaran albashinsu, gidajensu da sauran hakukuwansu. Binciken ilimin mata ta yadda zai gaggauta cikin gajeren lokaci, domin ci gaban qasa ba ya yiwo da hannu xaya. Mata da maza.
11. Gyara dokoki game da hana karvar rashawa saboda irin dokokin da jihohi suka yi yanzu game da wannan sai qara sanya karvar rashawa a voye suka yi. NEPU tana ganin cewa in dai za a kashe rashawa sosai, sai an yi *Raddul Mazalumi* tukun sai an yi *Min Aina Laka Haza*.
12. Shirya bankin manoman Nijeriya. Kafa dokoki sabbi game da gidajen sarautar gargajiya da niyyar a kange su daga guguwar zamani. Binciken tsofaffin gidajen sarauta da gidajen manyan malami da shahararrun mayaqa da raya sunayensu.
13. Shirya hanyar taimakon gajiyayyu da marasa galihu, 'yan tsuntuwa da marayu, makarantun Addini da masu sana'a ta gida, da shirya yadda sana'oinmu za su dace da zamani. [1]

Malam Aminu Kano, babban Shugaban NEPU, ya yi jawabi a rediyon Nijeriya, da Turanci, yana kiran mutanen Arewa su zavi 'yan NEPU su wakilce su a sabuwar Majalisar Nijeriya. Cikin jawabinsa ya ce ran 8 ga Agustan shekarar 1950 ne 'yan Samari kaxan, masu hangen nesa, suka ga lokaci ya yi a sami jam'iyyar mulki a Arewa. Su suka kafa NEPU. Ko da yake sunanta ya fi dangana ga jiha, amma waxanda suka kafa ta nufinsu jam'iyyar ta zama ta Nijeriya ne dukanta. Nufinsu su yi wani sabon tsari, wanda kowa zai zama dai-dai da kowa, ya sami 'yancinsa.

[1] GTK, 22/12/1954 shafi na 6

"A lokacin", in ji M. Aminu Kano, "NPC ba ta wuce kulob ta masu muhawara" ba. Ya ce, "Muhimmin abu, shi ne NEPU ba ta son rabo jiha jiha, kamar yadda muka gan shi yanzu a Nijeriya. Irin rabon da ta ke son a yi, shi ne wanda babu wani yankin da zai sami qarfin da zai ware kansa, ko sabili da qarfinsa da girmansa, ya riqa matsa wa sauran rabbai. Mun amince, in ana son Nijeriya ta zama babbar qasa ta Dimukuraxiyya, irin rabon da ya kamata a yi, shi ne ko waxanne jama'ar da ke da harshe da la'adu iri guda, sai a ware su wuri guda. Ta haka sai a sake raba qasar nan da yawa. Kowane kashi ya sami majalisarsa. Muna son gama kai ne, na ainihi, wanda zai xore."

Qungiyar NEPU an kafata ne da qudirin qwatar 'yancin talakawa daga Sarakunansu. Domin an zargesu da hanawa talakawa samun sakewa da jin daxin rayuwa. Saboda haka sai yaqin qwatar 'yanci ya yi bakin damo, 'yan NEPU na yaqar Sarakuna, 'yan boko kuma na yaqar Sarakuna. A qarshe talakawa ne suka rasa madafa, tattalin arziqin rayuwarsu ya tavarvare matsayinsu a qasarsu ya koma na bara da tumasanci.

NEPU qungiya ce da ke iqirarin qwatowa talaka wa 'yanci daga hannun masu sarauta, amma ba ta hanyar ba su ilimi da qarfafa sana'a, ta qarfi da yaji. Saboda haka babu mamaki yadda talakawa suka amsa kiran wannan qungiya na fitowa ayi gwagwarmayar qwato 'yanci daga Sarakuna. Don haka zaratan wannan qungiya suke talakawa ne, musamman 'yan tebur, da 'yan talla, da 'yan haya, da makanikai da teloli. Akasarin su kuma suka yi watsi da sana'o'insu don xaukaka wannan yaqi.

Har ila yau wannan jam'iyyar ta yi baqin jini ga Sarakuna da Turawan Mulki ainun. Saboda alaqarta da jam'iyyar NCNC wadda ta yi suna wajen siyasar tsageranci mai kuma neman mallakar wannan qasa ta kowane hali. Amma 'yan NEPU ko qaxan basu farga NCNC na amfani ne da su sai daga qarshe kan mage ya waye. Duk da haka rikice-rikicen da ke varkewa tsakanin NEPU da NPC ya daxe yana hana ruwa gudu a Arewa.

Wani abin takaici shi ne yadda talakawan suka yi watsi da sana'o'in su suka amsa kiran NEPU, wanda daga qarshe suka tashi a tutar babu 'yanci, babu kuma sana'a. Har yanzu a wannan matsayi ne akasarin talakawan Arewa suka sami kan su.

Tun kafuwar su Jam'iyyun Arewa ke bunqasa suke kafa abuta da qungiyoyi da Jam'iyyoyi daban-daban a ciki da wajen Arewa domin bunqasarsu da neman cimma muradunsu . a cikin wannan gwagwarmayar ne Firimiya ya qaddamar da Jam'iyyar NNA, a Kaduna, a qoqarinsa na neman sahalewar Siyasa a qasar nan

A ranar Sati 31 ga Oktoban shekarar 1964 da misalin qarfe huxu na Yamma (4pm), a Filin Wasa na Ahmadu Bello wato Ahmadu Bello Stadium a Kaduna ne Sardauna ya qaddamar da jam'iyyar Nigerian National Alliance (NNA). A

wannan rana ce filin wasan ya cika maqil da jama'a daga dukkan faxin wannan qasa. A wannan ranace kuma manyan 'yan siyasa daga jihohin wannan qasa suka halarci bikin qaddamar da wannan jam'iyya wanda Mai girma Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, G.C.O.N., K.B.E., LL.D., M.H.A., Sardaunan Sakkwato ya yi. Ga jawabinsa:

Bismillahir Rahamani Rahim

Shekara biyar ke nan wato a cikin shekarar 1959 da aka ba ku damar ku zavi gwamnatin da za ta yi wa qasar nan jagora zuwa ga samun 'yanci. A lokacin, ko da yake akwai alqawurra iri daban-daban kun yi zavi mafi kyau da ku ka ba N.P.C. kujeru masu yawa a Majalisar Wakilai ta Tarayya. Mun kafa gwamnati bayan mun qulla yarjejeniyar haxa gwiwa da N.C.N.C. Mun yi haka domin a lokacin mun amince da dattakon shugabannin N.C.N.C. Kamar yadda kowa dai ya sani shugabannin N.C.N.C. Kamar yadda kowa dai ya sani shugabancin wannan jam'iyya ya canja. Gogayyar da muka samu a shekarun nan biyar ta nuna mana cewa shugabancin N.C.N.C. yanzu yana da baki biyu, ba a iya amincewa da su, kuma ba aiki su ke yi tsakani da Allah ba don ci gaban Nijeriya. Bisa ga wannan zama na bugi sa bugi taiki da yaudara ba wanda zai yi baqin cikin vallewa da N.C.N.C. 'yan Nijeriya da yawa na kirki suna jin tsoron shiga sha'anonin gwamnati saboda gudun fallasa a cikin jaridun N.C.N.C. da rediyon N.C.N.C. da wuraren laccar N.C.N.C. Wai yanzu bayan sun yi aiki tare da mu shekara biyar sa'an nan ne suka gane mu muna da hanyar mulki irin wadda aka manta da ita, su kuma tasu ta 'yanci gaba ce. Sun sauko qasa qasa zuwa ga muqamin da babu wani mutumin kirki zai sauko har sun furta cewa suna iya abuta da Ibilis idan sun san zai kore mu daga fagen siyasar Nijeriya. Na tabbata da yardar Allah ba za su sami nasara ba kuma sun cancanci gazawar.

Ko kaxan ban so faxin waxannan maganganu ba saboda irin ban gaskiyar jam'iyyarta ga abokanta. Amma ya zama tilas ne saboda ganin irin abubuwan da suka gudana waxanda kowane xan Nijeriya ya sansu. Mun bi dukkan alqawurran da muka qulla da abokan yarjejeniyarmu, amma kash su ba su yi haka ba. Da zarar an soma sukar kowane al'amari da gwamnati ta shirya tare da su sai su ce su ba sa ciki, abin da ya fi muni kuma shi ne ba su kan fuskanci al'umma kamar mutanen kirki ba, a'a sai dai kowane lokaci suna qoqarin fid da kansu daga zargi. Wannan hali ne irin na yara ba halin manyan mutane da ke son su mallaki babbar qasa kamar Nijeriya ba. Babu makawa mu saki hannun juna da N.C.N.C. duk da son da ni ke yi ma

abokai sai dai na yi murna da rabuwarmu ta zo da sauri tun ba su riga sun qara vata mana sunan al'ummarmu ba da qasa ba.

Har yanzu mun amince cewa haxa qarfi wajibi ne idan Tarayyar Nijeriya za ta ci gaba da zama qasa xaya a cikin kwanciyar hankali. Tilas ne a sami abota da fahimtar juna tsakanin dukkan mutanen qasar nan ba tare da kulawa da jihohinsu ba. Saboda haka mun kafa sabon qawance da a ke kira "Nigerian National Alliance" wadda ta haxe dukkan jam'iyyoyin da ke qaunar ci gaban Nijeriya da zuciya xaya. A cikinu yanzu akwai dukkan masu kishin qasarsu waxanda buqatarsu kawai ita ce ci gaban wannan Tarayya. Mun yi wannan haxa gwiwa saboda haxa kai. Mun rungumi kowace qabila a kowace jiha. Za ku yi tambayar dalilin da ya sa mutane da yawa ko'ina a cikin Tarayyar Nijeriya suka amince da "Nigerian National Alliance." Amsa mai sauqi ce. Mun nuna masu gaskiyarmu da riqon amana da buqatummu da qoqarinmu na ci gaba a cikin kwanciyar hankali. Mutanen Nijeriya da na sauran duniya duka sun sani mukan dage ga manufarmu, kuma ba mu kan aikata komai ba don kawai mu daxaxa ran wasu mutane daga wajen qasarmu. Aikinmu shi ne mu riqi Nijeriya da kyau, yin haka kuwa shi zai ba Nijeriya abokai a wasu qasashe, abokan nan kuwa su ne abokanku mutanen Nijeriya.

Zai ba da sha'awa in an duba yadda qawancen su U.P.G.A. yake, N.C.N.C su ne manya a cikin U.P.G.A. Wannan jam'iyya kuwa ta nuna a bayyane rashin kulawarta a cikin al'amuran da suka shafi Nijeriya gaba xaya. Ta nuna cewa a cikin dukkan al'amura ta fi buqatar wata qungiya. N.C.N.C. ta nuna cewa ba ta da sha'awa a cikin al'amuran Jihar Yamma ko na wasu wurare a Jihar Gabas, balle ma Arewa. Wannan kuwa babu qage a ciki. Akwai ximbin dalilai, kuma manyan N.C.N.C. masu kan zargi junansu a kan haka. Idan har ana buqatar qarin bayani zan tuna maku da qoqarin N.C.N.C na muzanta Jihar Yamma da halakata, da danne tsirarun qabilu a Jihar Gabas da kuma baza asharararanci na qarya da qiyayya game da Arewa, da mutanenta da al'adunta. Abin da N.C.N.C. ke aikatawa ke nan domin kafa wani sabon Mulkin Mallaka. Na tabbata kuma mutanen Nijeriya ba za su karvi waxannan kaya da N.C.N.C. ke so ta xora masu ba.

To, su wanene kuma ke cikin U.P.G.A.? To, sai kuma Action Group da ke rai ga Allah. Kowa ya sani a da N.C.N.C. sun yi aiki gaya don su vadda sunan Action Group. Aikin N.C.N.C. ne ita kaxai ya kawo Action Group a cikin halin qasqanci da kunya wanda take ciki yanzu. Amma kamar yadda Hausawa ke cewa ne"qwarya ta bi

qwarya 'yar'uwarta." Ku tabbata ita ma N.C.N.C. ta kama hanya ne. Mutumin da ruwa zai ci ko kaifin takobi kamawa shi kai, a nan kuwa shi mutumin bai san ya kama gamsheqa ba wadda ba da daxewa ba za ta sare shi.

Abotar N.C.N.C. da Action Group ana renonta game da bala'in da ya far ma Shugabansu. An yi wa duniya alqawarin za a sake shi daga kurkuku da zarar U.P.G.A. sun hau gadon sarauta. A nan sai in ce "Action Group" sun cika wauta har ana wasa da hankalinsu. Da xai ba a tava sanin N.C.N.C. da wani aikin dattako ba, balle cika alqawari. Amma ya fi kyau "Action Group" su tambayi sabuwar qawarsu dalilin da ya sa wani Shugaban "Action Group", Mr. E.O. Eyo, mai laifin siyasa, ba a sake shi daga kurkuku ba. Me ya sa N.C.N.C. ta ga dai-dai ne a saki wani shugabanta wanda aka xaure saboda babban laifi? Ba shakka a cikin ruxun da "Action Group" su ke yanzu ba su ma amfani da dalili sai mafarki kawai su ke yi.

Dalilin qawancen N.C.N.C. da "Action Group" ba shi wuyar genewa. N.C.N.C. suna sane da cewa N.P.C. da abokanta ne suka hana su kawo mulkin shipta a Nijeriya. Saboda haka ne take qoqarin vata "Action Group" da mutanen Jihar Arewa da kuma sauran wasu mutane na Nijeriya. N.C.N.C. ta samu "Action Group" suna sauraren daxin bakinsu. Tun farko dai an kafa qawancen a kan harsashin qiyayya. Ana niyyar haddasa gaba tsakanin Kudu da Arewa. Ba don a haxa kan Nijeriya ba ne. Sa'ar da aka yi ita ce, akwai mutane masu hankali da suka gane cewa duk qawancen da aka yi nan gaba tsakanin 'yan Kudu da na Arewa yana da haxari kuma zai rushe mana Tarayya. Su mutanen nan su ne suke cikin qawancen "Nigerian National Alliance" kuma qungiyarsu ce kawai za ta agajemu daga son kan N.C.N.C.

Wata rana "Action Group" za su farga cewa an yaudare su ne ina fata kuwa ba za su yi fargar Jaji ba. Ya kamata mu riqi mutane da abubuwan da suka aikata. Aikin N.C.N.C. shi ne iya makirci da qulle-qulle da qage. A cikin shekaru biyar na qawancensu da N.P.C. kullum N.C.N.C. su kan nemi yabo a kan kowane abin qwarai da aka yi su nemi fita zargin kowane abu da aka yi maras farin jini komai qanqanta tai. Jaridunsu da rediyonsu lakkam suna suka da kada mutuncin N.P.C. da shugabanni na wasu sassa na Tarayya. Wannan kuwa sananniyar hanyar N.C.N.C. ce ta cin mutunci. 'yan Nijeriya da yawa waxanda ya kamata su amfani qasar nan, har da wasu manyan "Action Group", an rufe masu baki ta hanyar mugun halin N.C.N.C.

Qawancen N.C.N.C da Action Group a kan nau'i biyu hanyar da gwamnati za ta mallaki dukiyoyin qasa ba zai kawo wa Nijeriya gwamnatin kirki ba. Kafin in faxi dalili ya kamata in tuna maku cewa abin da jam'iyyoyin nan biyu su ke aikatawa ya fi komai nisanta daga niyyarsu. Cike su ke da mutane masu haxama da son tara dukiya, waxanda ke iya bin kowace irin hanya mai kyau ko mugunya don su sami arziqi da iko. Ba a tava lalata niyyar mallakawa gwamnati ikon dukiyoyin jama'a irin haka ba. Na faxi cewa mutanen N.C.N.C. da na "Action Group" ba za su iya kafa maku gwamnatin kirki ba kuma kun san haka tun daga aikace-aikacensu. A da "Action Group" su ke da gwamnati a Jihar Yamma. Ta ci nasara wajen al'mubazzarta kuxaxen Jihar har an rushe ta. Hukumomin bincike da Kotunan shari'a sun tabbatar da irin halakar da masu son su ci duniya su kaxai suka jawo wa Jihar Yamma. Ita ma N.C.N.C. an tava yi mata binciken kanta wanda ya nuna "Action Group" ba ta fi ta lalacewa da komai ba. An yi sa'a abokanmu N.N.D.P. ce ke ceton Jihar Yamma a halin yanzu na kuma tabbata idan su ma mutanen Jihar Gabas sun amince da abokanmu za su sami nasu ceton.

Kada a yi wani kuskure. Ba cinye kuxin gwamnati ne kawai kasawar jam'iyyoyin nan biyu ba. Duka sun kasa kafa wa mutanensu Gwamnatoci katamamma. "Action Group" ta kawo ruxu da yamutsi, a Jihar Yamma, kuma abokansu N.C.N.C. su ne suka fara kamasu da laifin. A Jihar Gabas kuwa ba a tava samun zama lafiya ba. A kan danne tsirarrun qabilu a hana su haqqinsu na 'yan-Adam. To, yaya abutar waxannan jam'iyyoyi za ta amfani Nijeriya. Na tabbata ba za ta yi ba!

Haka kuma U.P.G.A suna da 'yan kurkuku wai su 'Northern Progressive Front'. Mutane da yawa a Kudu ma suna mamakin abin da zai sa wani mutumin Arewa zai shiga qawance da wanda yake niyyarsa ita ce kawai kawo qiyayya tsakanin Kudu da Arewa. Babu abin mamaki! Ku dubi mutanen da ke cikin N.P.F. Qungiyar da su ke ci gabansu shi ne su baza ruxu kuma ba su iya komai sai zage zage. Jama'armu sun sani 'yan qungiyar nan ba su kawo komai ba sai tashin hankali a Arewa kuma ba su ganin darajar abubuwanmu na gado. Ana sane da cewa 'yan qungiyan nan su kan yi komi da zai vata zaman lafiya a Arewa. Shekara da shekaru ba su komai sai zagin hanyoyin Sarauta na qasar nan komai kyawonsu. Da su da abokansu "Action Group" da N.C.N.C. suna so mu bar hanyoyimmu na gargajiya mu xauki hanyoyin da su ke baqi ga qasar Afirka. Sun sami masoya a wasu qasashe saboda labarun da su ke bazawa na qarya

amma har yanzu ba su sami masoya a gida ba. Mun sani ana amfani da su ne kamar gugar ya sa yadda buqatar iyayen gidansu za ta biya don su mallaki dukkan Nijeriya. Me ya sa su ke bari ana amfani da su ta wannan mummunar hanya? Ina tabbata maku cewa ba saboda buqatar haxa kan Nijeriya ba ne. Wato sana'a ce kawai. Kamar yadda suka yaudari mutane a qasashen waje suna gaya masu abin da ba su iya aikatawa haka kuma su ke cutar N.C.N.C. da Action Grop da cewa suna da magoya baya alhali kuwa ba su da su.

Bai ma kamata a kama maganar "Northen Progressive Front" ba, tun ma ba Arewa ba. Misali xaya shi ne 'yar qungiyar N.P.F., tun ma ba N.E.P.U. ba, sun daxe suna cewa 'yan'uwansu na Arewa ba su cin gaba. Ba su tava yabon abubuwan Arewa ba. Su kan wulaqanta hanyoyin Arewa na gargajiya, tun ba Sarakuna ba. Yanzu kuwa sun sake ra'ayi. Su kan ce su ne masu son hanyoyin Arewa. Su kan yabi Sarakuna suna kai da kawo da saqon neman goyon bayan Sarakuna da alqawurra na qarya.

Tun kafa N.E.P.U. ba ta komi sai sukar Sarakuna xai xai amma duk lokacin da suka sami dama su kan bayyana su ne masu qaunar Sarakuna a kan al'amuran da suka sha bambam da niyyarsu. Wannan rashin tsayuwa a kan manufa ba ita ce za ta kawo wa Arewa irin gwamnatin da take buqata ba. Amma qila don ita jam'iyyar ba ta tava tunanin za ta kafa gwamnati ba. Ba ta da mutanen da suka dace kuma ba ta da hali. An kafa ta ne kawai saboda jidali da damuwar hukuma da hana ci gaba.

Waxannan su ne suka taru suka kafa U.P.G.A., amma kuma ba su da wadar zuci. An gaya mana wai wannan qawancen da N.C.N.C. ke yi wa jagora ne za su sa gwamnati ta mallaki dukkan dukiyoyin Nijeriya. Amma har yanzu ba su tsaya a kan irin hanyar "socialism" da za su bi ba. N.C.N.C. da tasu hanyar, Action Group da tasu, N.E.P.U. ce ba su faxi irin tasu ba. Kowace hanya da aka zava ina tabbatar maku cewa ba za ta yi aiki a Nijeriya ba. Domin jam'iyyoyin U.P.G.A. ba su da buqata da haka. Su masu cewa wai suna so gwamnati ta mallaki dukkan dukiya sun fi kowa arziqi a Nijeriya. Lokacin da aka ba su damar yi wa qasar nan aiki sai suka yi aikin yadda zai amfanesu su kaxai da abokansu da dangoginsu. Lokacin da suka sami mulki sai suka watsad da aiki da daraja suka xauki samun duniya. Ina baqin cikin faxar waxannan maganganu amma kun san duk gaskiya ce ni kuma ba zan iya kaucewa gaskiya ba.

Jam'iyyoyin U.P.G.A. sun nemi gwamnati ta karve dukkan sana'o'i musamman aikin haqar kuza a Lardin Plateau. Kada wannan buqatar

ta yaudari kowa. Masu wannan qawance sun fi kowa jari a Nijeriya ba kuwa da zuciya xaya su ke cewa gwamnati ta karve dukiyar baqi a bar masu tasu ba. A wajen "Nigerian National Alliance" kuwa du kan masu jari, baqi da 'yan qasa muna tabbata musu cewa ba mu yarda da qwace ba. Za a bar wa kowa jarinsa kuma za a qara masu qarfin amfani da jarin don kyautata Nijeriya. Za a nemi qarin jarin gwamnati a cikin ayyukan sana'o'i da ciniki da noma. Ba mu ga wani aibi ba a cikin kowane irin jari ko na mutum ko na gwamnati, ba kuwa za mu kwaikwayi waxanda ke ganin laifi ido rufe ba. Kowane yana da amfaninsa, kuma muddinsa, kuma muddin an yi amfani da su yadda ya kamata za su yi gudunmawa ga qaruwar arziqimmu.

Wajen ma'amala da sauran al'ummomi kuwa gwamnatin Tarayya a qarqashin "Nigerian National Alliance" za ta xauki hanyar 'Yan ba ruwammu. "Za mu zayyana kyakkyawar surar Nijeriya ta hanyar qulla abota da dukkan qasashe da mutane. Mu'amalar mu da qasashen waje kullum za ta kasance a madadin Nijeriya. Ba za mu yi amfani da muqamimmu ba don mu sami taimakon wata qasa saboda rushe wani al'amari na Nijeriya kowata jam'iyya ba kamar yadda U.P.G.A. su ke yi. Amma abubuwan da a ke aikatawa da waxanda a ke faxi su kan qaryata haka. A cikin shekarar 1959 Action Group sun yi yaqin neman zave bisa ga manufar abota da qasashen Yamma. Da ba su ci zave ba sai suka xauki manufar "Democratic Socialism", wato gwamnati ta karve dukkan dukiyoyi ta hanyar domokuraxiyya da manufar "baruwammu", wato dai niyyarsu ita ce su sami goyon bayan baqi bisa ga 'yan'uwansu mutanen Nijeriya. Kada qasar nan ta kuskura ta zavi U.P.G.A. domin qungiya ce ta mutanen da sauran qasashen duniya ba su amincewa ba. Nijeriya tana buqatar abota da goyon bayan wasu qasashe, amma U.P.G.A. sai maqiya take jawowa Nijeriya. Wasu al'ummomi ba su son su domin ba su da sanin ya kamata ga tsiwa kuma duk lokacin da suka fita Nijeriya su kan nuna wa duniya cewa sun fi son kansu da Tarayyar Nijeriya. Ku dubi yadda suka riqa manufar ba ruwammu. Su 'yan N.C.N.C. da "Action Group" su kan aika da 'ya'yansu karatu a Ingila da Amirka. Mu muna ba 'ya'yammu ilimi a Nijeriya. Kowa ya san gwamnatin Jihar Gabas ba takan aika xalibai qasashen Gabashin Turai ba. Ba da daxewa ba sun aiki wani wakilinsu zuwa qasashen Kwaminis ya gargaxi xaliban da ke can kada su koyi maqarqashiya. Amma ba su yi wa xalibansu da ke qasashen Yamma irin wannan gargaxi ba. A qarqashin N.P.C. gwamnatin Tarayya takan aika xalibai ko ina a cikin duniya har tana

taimakon qasar Russia wajen xaukar 'yan Nijeriya aiki lokacin da aka buqaci haka.

A cikin Afirka U.P.G.A. sun kayad da girman Nijeriya. Saboda rashin kan gadonsu dangantaka tsakanimmu da wasu qasashen Afirka ta Yamma ta lalace alhali kuwa qasashen nan ne ya kamata su zama manyan abokammu. Su kan wulaqanta 'yan O.A.U. ba tare da wani dalili mai qarfi ba, kuma ba su iya sulhu ba. Saboda haka U.P.G.A. ba ta da wata manufa game da al'amuran qasashen waje. Idan mutanen Nijeriya sun zave ta abin zai wahalad da Nijeriya a cikin sauran duniya. Bari mu xauki misali da sha'anin Afrika musamman, mene ne suka yi game da dangantakar Nijeriya da sauran qasashen Afirka? Dubi vavatun da suka yi wa Ghana. Dubi qaryar da suka yi wa abokiyarmu Jumhuriyar Nijar ba gaira ba dalili. Ku dubi shakiyancin da suka yi wa Masar da Sudan. A ina suka tsaya game da manyan matsaloli irin su Congo? Ba su da kangado. Kullum sai faxa da ashar da shakiyanci. Kullum suna lave a shinge sai sun ga gefen da farin jini yake su tsallaka can. Ba su damu da wurin da gaskiya take ba ko hankali. Ba su riqon al'amuran qasashen waje zai rushe dukkan abin da muka shekara biyar muna ginawa.

Wajen qaruwar arziqi kuwa "Nigerian National Alliance" ne kawai za su shirya wa Nijeriya tabbatacciyar manufa wadda za a tafi da ita bisa hanyar gaskiya. Idan akwai mai shakka sai ya dubi abubuwan da muka yi a Arewa da Yamma. Muna kyautata arziqin jihohin nan kuma muna tare da mutane domin mun yi imani da cewa saboda jama'a a ke son ci gabansu ba saboda 'yan siyasa kaxai da abokansu ba. Mun yarda da haxa gwiwa na sosai saboda ci gaba da qaruwar arziqin Nijeriya. Me masu adawa da mu suka yi a kan haka?

Nigerian National Alliance" suna da kyakkyawar aniya game da al'amuran da suka shafi shirin mulki. 'Yan Nijeriya ne suka tsara shirin mulki bisa ga wasu sharuxxa. Idan sharuxxan sun canja tilas ne shirin mulkin ya sake amma ba za mu yarda da wani canji ba a kan dabarun da ba su dace da Nijeriya ba. An gaya mana wai idan U.P.G.A. sun sami mulki (wanda ba za su samu ba, da yardar Allah) za su canja shirin mulki a sami Shugaba mai ikon gudanar da komai. Qawancemmu yana ganin cewa muqamin Shugaba mawuyaci ne. Shi uba ne ga dukkan al'umma don haka tilas ne a tsare shi daga dukkan abin da zai jefa shi a cikin qazamar siyasa. Idan an ba shi ikon gudanar da komai ba za a iya tsare shi daga tazniya ba. Amma kuma idan akwai buqatar a sami Shugaba mai ikon gudanar da al'amura tilas ne a zave shi ta hanyar ba da damar jefa quri'a ga mafi yawan

mutane. Amma ba nufin N.C.N.C. ke nan ba, so take a ba Shugaba iko ba tare da yardar masu zave ba. Haka kuma tana so ta yaudari qawayenta na cikin U.P.G.A. domin idan N.C.N.C. za ta zavi Shugaba mai cikakken iko ba za a zave shi daga cikin Action Group ba balle N.E.P.U.

To, jama'a bayan waxannan 'yan maganganu zan ba ku alqawurran da Jam'iyyun qawancemmu suka yi. Alqawarin na haxa kai da haxa gwiwa ne. An lura da dukkan ra'ayoyi. Mun tsara shi ne saboda Nijeriya da fa'idar mutanen Nijeriya. Ba don wata qungiya ba. Dukkan 'yan Nigerian masu hankali za su yarda da shirye-shiryen da ke ciki su karve su. Na tabbata idan mun yi aiki da abin da aka shirya za mu kawo wani sabon zamani na arziqi da zaman lafiya. Kuma na tabbata muna da mutanen da za su gudanar da shirye-shiryen da zuciya xaya da kuma qarfin hali. Ku dubi Shugaban Sashin Tarayya na "Nigerian national Alliance", Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa. Shi mutum ne da ya nuna maku cewa ana iya dogara gare shi, mai haquri ne, mai wayo kuma babu son zuciya. Duk duniya an yarda da cewa yana cikin manyan Shugabanni da aka tava samu a cikin 'yantattun qasashen Afirka. Me mu ke da shi a cikin U.P.G.A.? Kun dai san su qwarai. Ku ba ku iya amincewa da su. duniya ma ba ta amince da su ba. Sun yi gaira a kowane lokaci. An san su da rashin cika alqawari. Af ba mu ma san wanda zai zama Shugaban 'yan Adawa ba domin muqamin da U.P.G.A. za su samu ke nan a cikin sabuwar Majalisar Tarayya da yardar Allah.

'Yan'uwa, inan roqonku ku amince da "Nigerian National Alliance" kuna iya dogara garemu mu tafiyar da al'amuranku da zuciya xaya cikin girmamawa. Na tabbata "Nigerian National Alliance" ita ce kawai za ta ja Nijeriya bisa haxa kai a cikin mawuyacin lokacin da ke gabammu. Har wa yau ina roqonku ku yi amfani da hankalin nan na ku, ku zavi "Nigerian National Alliance" su kafa gwamnatin Tarrayya.

Allah shi taimake mu duka, Amin.[1]

Rikirkitaccen Zamani

Qaddamar da wannan jam'iyya da Sardauna ya yi ba qaramin tayar da hankalin 'yan Kudu ya yi ba. Saboda nuna gwaninta da bijintar siyasar Sardauna ya sanya manyan jam'iyyun Kudu guda biyu, AG and NCNC ke dushewa matuqar gaske kuma cikin hanzari. A wannan lokaci da AG ke tavarvArewa Cif. Awolowo

[1] A.H/CP/SA/A36

yana gidan Yari saboda an kama shi da cin amanar qasarsa. Abutar jam'iyyar NPC da NNDP tayi qarfi sosai. A dalilin haka ne sai 'yan Kudu suka firgita sosai suka shiga furofagandar cewa Sardauna zai mamaye Kudu ya kuma mallake ta saboda shirinsa na kafa Daular Sardauna. A wannan lokaci jam'iyyar NPC na ragargaza sauran jam'iyyu a siyasar qasa baki xaya.

A siyasar jiha kuwa, NPC na fama da hamayyar jam'iyyar NEPU wadda ta yi qaurin suna wajen qiyayya da Sarakuna. Amma duk da haka jam'iyyar NPC sai ta zama sakaina mai iya ruwa a tekun siyasar Nijeriya a wani hali mawuyaci. Duk da haka gwagwarmayar neman sahalewar Siyasa sai qara qarfi ta ke

Jam'iyyun NEPU da NPC sun farkadda 'yan Arewa harkar siyasa amma kuma aikace-aikacensu, musamman qungiyar NEPU sun haifarda Tsageranci a Siyasa. Irin wannan salo na siyasa ya raunana haxin kan jama'a ya kuma assasa siyasar Adawa da gaba a siyasa. Kamar yadda aka bayyana ne an yi amfani da jam'iyyar NEPU wajen cimma nasarar yaqin qwatar 'yanci da wasu masu ilimin zamani suka aiwatar. Jam'iyyar NCNC ta yi amfani da 'yan NEPU wajen dasa siyasar Tsageranci a Arewa, a qoqarinta na neman mallake wannan Jiha ta kowane hali. Har-ila-yau Turawan Mulki sun yi amfani da NEPU wajen kawo wa NPC cikas domin a hargitsa siyasar Arewa. Alhaji Tanko Yakasai sanannan xan NEPU ya bayyana wannan al'amari inda ya ce:

Turawan Mulki sun yi imani da cewar idan aka bar jam'iyyar mutanen Arewa ta qafu a qungiyar siyasa zata iya zaburar da 'yan Arewa su yiwa gwamnatinsu da mabiyansu da mulkin En'e bore, wanda ka iya hanzarta kawo qarshen mulkinsu a Nijeriya. Abin da ya tayar wa da Turawa hankali shi ne qoqarin wannan qungiyana zama jam'iyyar siyasa da kuma sunanta "Northern Peoples Congress" wanda ya yi kamada na qasar Indiya mai suna "Congress Party of India." Turawan sun fi tsanar Malam Sa'adu Zungur, da Malam Aminu Kano da Isa Wali, saboda ilimi da wayewar kansu. Bugu da qari ma qasar Indiya ta samu 'yanci ne a shekarar 1947 wanda ya zo kusa da shekarar da aka kafa Jam'iyyar Mutanen Arewa. Har ila yau a dai-dai wannan lokaci ne Daular Birtaniya wato *British Empire* ta fara xurkushewa bayan ta samu shekaru masu yawa tana mulkin duniya.

Qasar Ingila na gunagunin rasa qasar Indiya da ta yi wadda ita ce qasa mafi girma da yawan mutane ba a nahiyar Asiya ba har ma a duniya baki xayi saboda haka sai suka tsaya tsayin daka don suga basu rasa wata qasaitacciyar qasa mai yawan mutane a Nahiyar Afrika ba wadda itace Nijeriya. Domin cimma wannan manufa sai Turawan mulki da haxin ka abokansu da ke cikin mulkin En'e suka haxa qarfi da qarfe don suga wannan jam'iyyar bata zama ta siyasa ba.[1]

[1] Tanko Yakasai: *The Story of A Humble Life: An Autobiography, Vol. 1, shafi na 46.*

Duk da qokarin da Turawa suka yi na dakushe qarfin siyasa a Arewa sai da wannan tsiro ya fito ya kuma yi ice mai rassa guda biyu: NPC da NEPU. A shekarar 1952, jam'iyyar NEPU ta buxe wani sabon falle a tarihi saboda daga wannan shekara ce ta duqufa wajen yaqinta na Neman Sawaba. Turawan mulki sun hasala sosai saboda nasarar da qungiya NEPU ta samu a zavukan shekarar 1951. Tun daga wannan, lokaci ne suka fara xaukar tsauraran matakai a kan 'yan wannan qungiya don a dakushe yaxuwarta a Arewa. Kafin wannan lokaci kuwa akwai kyakkyawan jituwa a tsakanin Sarakuna da 'yan NEPU duk da suna su kan mulkin En'e.[1]

Saboda haka rashin jituwa ya hudo kai tsakanin Sarakuna da 'yan NEPU Turawan Mulki ne suka haddasa shi don su cimma manufofinsa na Mulkin Mallaka. A dalilin haka ana iya cewa rigingimun da suka riqa harkewa a tsakaninsu, yaqi ne na 'yan NEPU da Turawan mulki amma sai suka yi amfani da Sarakuna a matsayin garkuwansu. A wannan shiri ne, Alhaji Tanko Yakasai ya bayyana cewa:

A zambar farko da Turawan Mulki suka yi shi ne sai suka zuga Sarakuna da shugabanni a Arewa cewa jam'iyyar NEPU ta fito ne domin ta kifar da mulkin En'e su kuma darkake mulkin Sarakuna. Sun kuma qara harzuqa Sarakuna da lafazozin da shugabannin 'yan NEPU ke yi a kan danne talaka da ake yi."[2] Babu shakka Sarakuna za su yarda da wannan zugar domin ai biri ya yi kama da mutum. Domin tun kafin qungiyar NEPU ta taso, akwai shirin COBA a qasa da ke neman hanyar kifar da mulkin Sarakuna a Arewa. Da garwashin wutar wannan tsohon shiri ya ruru sosai ne sai harshen wuta ya fito ta qungiyar NEPU. 'Yan COBA ba kukan mulkin danniya da zalunci suke wa mulkin Sarakuna ba, a'a, qorafinsu akan mulkin En'e shi ne ya kankame ko'ina. Yakasai ya jaddada wannan qorafi, inda yace: "Qarfin ikon mulkin En'e nada faxin gaske. Sarakuna ne ke tafiyar da shari'a da bada doka, suke bad a hukunce-hukunce, da mallakar qasa da gandun daji, da kula da tsafta, da lafiyar dabbobi da tafiyar da ilimin Firamare da Sakandare, da harkokin gargajiya, da karvar haraji da jangali da kula da kasuwanni da kula da lafiyar jama'a da makamantansu. Saboda haka mutane da ke aiki a qarqashin a kowace En'e sun kai dubbai yawansu kwatankwashin girmanta.

En'e ta Kano, ita ce mafi girma da yawan mutane itace kuma mafi arziqi idan aka yi la'akari da kudaxen shigar da take samu, ma'aikatanta ma sun fi na kowace En'e samun albashi mai tsoka. Haka kuma biyayyar dubban waxannan ma'aikata a wannan tsari nag a Sarki ko shugaba ne kacokan. Amma saboda biyayyar

---

[1] Tanko Yakasai: *The Story of A Humble Life: An Autobiography, Vol. 1, shafi na* 56

[2] *Ibid., shafi na 46.*

mutum guda ake awa don haka sai wannan tsari yaba da kafar yin tumasanci da zalunci da danniya."[1]

A lokacin da 'yan adawa ke qorafin mulkin Sarakuna ya kankame komai, suke qorafin cewa kamar Sarkin Kano mutum fiye da miliyan uku ke biyayya gare shi, a wannan lokaci ne Sarauniyar Ingila mutum miliyan saba'in da huxu ke biyayya gare ta a qarqashin Mulkin Qasashenta. To, an ce idan bango ya tsage ne qadangare ke samun qofar shiga. Da aka samu babbar varaka a tsakanin jam'iyyar NEPU da Sarakuna sai Turawa suka sami dammar assasasa shirinsu na *Divide et impera*. A wannan lokaci sai su tunzura Sarakuna suna cewa dasu, "kada ku yarda da 'yan NEPU don za su kifar da mulkin Sarakuna. Idon kuma suka sadu da shugabannin 'yan NEPU sai suce das u, "kada ku yarda da zaluncin Sarakuna wanda mulkin mutum guda wato Sarki ke haddasawa. Ku dubi gari kamar Birnin Kano, a ce mutane miliyan uku su riqa bin mutum guda sau da qafa?"

Makircin Turawan Mulki sai ya yi mummunan tasiri akan shugabannin NPC da NEPU don haka sai suka shiga yin karon barta da junansu talakawa kuma suka shiga halin qaqani-kayi. Amma ba kamar 'Yan NEPU waxanda suka yi watsi da ilimi da sana'a lokacin da suka bazama wajen yaqin neman 'Yanci. A wannan lokaci ne kuma Cif Obafemi Awolowo ya farkar da Yarbawa da su riqe ilimi da sana'a don qwatar 'yancinsu. Suka kuma amsa kiransa baki xaya, wanda har yanzu ba su sassauta riqon da suka yi wa ilimi da sana'a ba. Ita qungiyar NEPU ta yi imani da cewa zata iya qwatar mulki da qarfi wato *Coup D'Etat*, daga hannun Sarakuna da Turawan Mulki. Duk da cewa tana da rauni sosai na rashin kuxi da manyan mutane. Bugu da qari ma ta 'yan Rawan Sawaba NEPU ke samun kuxin tafiyar da harkokinta.[2] Waxannan samari da Yammata ne waxanda suka shahara suka kuma shagala wajen rawan goge da banjo, amma ba wajen ilimi da sana'a ba, ko da samun ilimi sai xan-gatata a wannan lokaci amma koyon sana'a da ci da gumin kai abu ne mai sauqi ga kowa.

A wannan lokaci har su kan riqa rera waqar 'yanci wadda shugabansu Malam Aminu Kano ya wallafa suka riqa rerawa: Ga waqar Yanci:

Ya Ta'ala Jallah Sarkin rahama,
Gamu mun taso da halin azama,
Taimako na gunka Sarki mai sama,
Don mu san 'yanci da adalcin zama.
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya.
Mun nufato bamu tsoron wahala,

---

[1] Tanko Yakasai: *The Story of A Humble Life: An Autobiography, Vol. 1, shafi na* 57

[2] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*, shafi na 53

Gafara sa duk mutum mai gafala,
Lokacin yau namu ne ba shagala,
Za mu san komai mu jure wahala.
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya .

Za mu ture dukiya har rayuka,
Mu na yau 'yan yau mazajen ayyuka,
Kan tafarki mustaqimi mun zaka,
Haggyalan duk masu danne tal aka,
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya.

Zamani ya juyo komai na jiya,
Mun ruga mun xauki tutar juriya,
Don mu ceto Ummuna Nijeriya,
Har mu bar suna a wannan duniya,
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya,
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya,
Ya Ta'ala Jallah ga Nijeriya.[1]

Ruguntsimin yaqin neman wannan 'yanci ne ya haifar da rikirkitacciyar siyasa a Arewa. Shi ne kuma ya jefa dubban talakawa cikin masifu iri-iri. A kowane zamani yunqurin qwatar mulki, wato Coup D'Etat abu ne mai haxarin gaske. Ana yanke duk wanda aka samu da wannan laifi hukuncin kisa. A wannan mawuyacin lokaci ne 'yan NEPU a wannan waqa suka ci alwashin cewar "Za mu sau komai mu jure wahala", a fafitikar neman 'yanci. Haka kuma sun xauki alwashin, "za mu ture dukiya har rayuka." Saboda haka ba wanda ya yi mamakin ganin yadda su ka yi watsi da ilimi da sana'a a fagauniyar bixar 'yancinsu. Babu kuma wanda ya yi mamakin ganin yadda Sarakuna suka riqa gasa wa 'yan wannan Jam'iyya gurjiya a hannu, a gwagwarmayar kare mulkinsu. Malam Sa'adu Zungur ya fahimci *Indirect Rule* sosai da sosai, ya kuma gane Sarakuna basu da ikon zartar da komai sai abin da Turawan Mulki suka gabatar mai kyau ko mara kyau. A waqarsa *Jihadin Neman Sawaba* ya bayyana wannan mummunan tsari, inda ya ce:

Ka ji sharru tsakanin NPC
Da baturen mulki addakari
Sun qulla abota ba rabuwa
Sai ran da gizami ya gaji gari
Daula xaya ce ikon uku ne

[1] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*, shafi na 102

Tsarkiya uku duk a bakar garari.[1]

Irin wannan mulki mai "Daula Xaya" amma mai "Iko Uku", ita ta haifar da siyasar gaba da tsageranci a Arewa. Waxannan baitoci sun fassara qwayar da ke qunshe a tsarin mulkin *Indirect Rule* wanda ya misalta shi da Tsarkiya uku. A kuma sauran baitatocin ya bayyana matsayin Sarakuna a cikin wannan tsari, inda ya ce:

An ce ikon komai na gun
Sarki wai don shi ke da gari

Amma Razdan Di'o da waninsu
Duk mashawarta ne ba garari

Qaryan banza qaryan wofi
Su ke da zare su ke waxari

Ai sarakai kam hotanni ne
Na sarautar al'ada a gari

Razdan, Di'o da su ADO
Su ke da mabuxin al'amari

Su ke da wuqa su ke fixar
Mulkin jama'a bisa kan garari.[2]

Malam Sa'adu Zungur ya faxakar da 'yan Arewa a waqoqinsa haxarin 'Daula Xaya Iko Uku' wadda ba shakka ita ta kawo harqiyar mulkin Sarakuna a Arewa. Ita ce kuma ta haddasa Siyasar Tsageranci. Amma duk da cewa 'yan qungiyarsa sun fahimci irin wannan rikirtaccen zamani amma a maimakon su sake salon gwagwarmayarsu sai suka take saninsu suka yi wa Sarakuna alkafira, a wannan rikitaccen zamani wanda ya haifar da Daula Xaya Iko Uku!

Daula Xaya Iko Uku

---

[1] A. M. Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na 378

[2] *Ibid.*, shafi na 380

Alhaji Muhammadu A. Jumare, a littafinsa mai suna *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa*, ya faxakar da 'yan Arewa illolin Mulkin Mallaka a Arewa. Haka kuma ya bayyana dalla-dalla yadda aka kirqiro "Daula xaya Mai Iko Uku." Akan haka ne yace: Abin lura a nan shi ne daga lokacin Turawa ne kaya ya fara kwancewa, a inda suka shimfixa tsarin daularsu na Mulkin Mallaka, tare da kau da al'adar mulkin da jama'a suka saba da shi na kaifi guda, wato iko xaya a kowane wuri da lokaci. A nan ba wai ana nufin Turawa sun yi abin da bai kamata ba ne, in aka yi la'akari da aqidar karvar mulkinsu na baqi masu tashi idan "kasuwa ta ci ta watse." qare-qaren da Turawa suka yi a dukan jihohin Nijeriya guda uku, wato Arewa, Yamma da Gabas su ne:

i. Larduna, waxanda suka qunshi qasashen Sarakuna fiye da xaya. A nan akan ajiye Bature da sarautar Razdan a matsayin wakilin gwamnati.
ii. Kowace qasar Sarki aka manna wani Baturen mai Sarautar Babban Jami'in Mulki (SDO) wanda yake da ruwa da tsaki, tare da ikon sa baki da hannu a komai, na tafiyar da mulkin jama'a fiye da Sarki.
iii. Aka kafa Majalisar Sarakuna ta jiha, wadda ba jama'a za su zava ba, domin bai wa Gwamna shawara (ko da yake shi Gwamna ya fi aikida shawarwarin Razdojinsa Turawa).
iv. Aka qirqiro"Bariki, Zangon Turawa" aka sa Bature da Sarautar Kantoma, domin lura da wurin da aka shirya tsarin tafiyar da qananan Hukumomi irin na Ingila, An yi wannan ne domin a kiyaye Turawa daga cututtuka tare da kare su daga 'yan qasa waxanda aka xauka dabbobi, kuma a tabbatar rayuwar Bature an fifita ta fiye da yadda yake rayuwa a Ingila domin a xokantar da su su zo Nijeriya.
v. Aka kafa wata qungiyar Tarayyar En'e da ta qunshi qasashe fiye da biyu, wai domin su yi aiki tare. Aka kuma sa babban jami'in Mulki, Bature, (SDO), shi ne shugaba, kuma mai hukunta komai, sai dai loto-loto ya ba Razdan rahoto. Sarakuna, manyan malamai da manyan attajirai su ne wakilai na wannan Majalisa bisa naxin Turawa ba zaven jama'a ba.
vi. A birane aka qirqiro Majalisun Birni bayan na gunduma. Jami'in Mulki Bature, Di'o, da taimakon Hakimi su ke lura da ita wannan majalisa ta gamin guiwa. Hakimi shi ne shugaban Majalisar, amma Di'o shi ne ke da ikon yanke hukunci.
vii. Har ila yau, aka qirqiro Majalisun Waje waxanda suka qunshi gundumomi fiye da biyu, wanda aka sa Di'o ya lura da su, a matsayin,"mai wuqa, mai nama."
viii. Kowace gunduma an sa Di'o ya lura da ita.
ix. qasashen manyan Sarakuna kuma aka kira su En'e – En'e. Wato:

a. A lokacin daular Have qasashe na Sarakuna guda 14 ne duka har da Daura. A hakunce an yi masu laqabin Hausa Bakwai da Banza Bakwai. "Hausa" inda akwai Hausawa kuma ana addinin musulunci, "Banza" kuwa qabilun da ba Hausawa ba ne, kuma mafiya yawa masu addinin gargajiya.
b. A lokacin daular Fulani sai aka mayar da qasashen Sarakuna suka zama 13. Rano, wadda a da masarauta ce kamar kowace sai aka haxa ta da Kano a matsayin gunduma.
c. A daular Turawa sai aka samu larduna 13, kamar yadda Fulani suka tafiyar da nasu mulkin. Amma sai aka qara qasashen Sarakuna daga 13 zuwa 88. Aka kuma qirqira En'e – En'e qarqashin Di'o – Di'o da qasashen sarkakuna guda 69. A bisa tsarin har ila yau aka tsaga qasashen a matsayin gundumomi a inda aka samu gundumomi 552. A nan aka nesanta talaka da mulki kuma aka ruxar da shi na rashin fahimtar wane ne wane tsakanin Sarki da S.D.O ko D.O. ko kuma wace matakalar hukuma ke aiwatar da wani aiki.[1]

Wannan mummunan tsarin mulki ne Malam Sa'adu Zungur ya kira, "Tsarkiya uku duk a bakar garari." Shi kuwa Dr. Mohammed Jumare ya bayyana wannan illar da *Indirect Rule* ya haifar, a inda ya ce: "Turawan Ingilishi, ganin ba sun zo zama ba ne, kuma su ba 'yan qasa ba ne, ga shi kuma ba su da yawan da za su cike dukan muqaman tafiyar da mulki, wato daga tarayya ya zuwa shugabancin taruwar jama'ar gari, sai suka qago nasu sabon salon mulkin, inda aka canza wa Sarakuna matsayi, daga masu mulki zuwa ga yan – barandan masu mulki – Turawa. Yin haka ya sa an qirqira wa jama'a abin da a iya kiransa, "Da naka na jikin ka ake kashe ka", wato a yi qotar gatari da itace a sare itace da ita. Wani Baturen Ingilishi, tsohon soja, wanda aka naxa a matsayin Gwamna Jihar Arewa mai suna Lord Lugard shi ne ya fara shimfixa irin wannan tsari mai suna "Mulki a Fakaice."[2]

Wannan tsarin Mulki a fakaice ko *Indirect Rule* shi ne ya wanzar da Tsarkiya Uku wadda taiwa Arewa mummunar xauri tun daga wancan zamani har yanzu. Ko da yake kowa ya san Sarakuna basu da ikon zartar da hukunce yadda ya kamata amma sai masu ilimin zamani suka xora masu laifin illolin da mulki a fakaice ke haifarwa don su vata su a idon jama'arsu saboda wata manufa ta siyasa. Dr. Jumare ya bayyana illolin shirin "Da naka na jikinka ake kashe ka", inda ya ce:

---

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa*, Ahmadu Bello University, Press Ltd. Zaria (2008), shafi na . 299-301

[2] *Ibid*., shafi na 297

"Abin da wannan ya haifar shi ne, aka nesanta talaka da mulki. Haka nan domin Sarakuna, Hakimai da Dagatai su nuna wa jama'a cewa dai har yanzu su ne ke yi, sai suka shiga gallaza wa jama'a, domin su tabbatar da ikonsu da mulkinsu. Suka zama wasu "Fir'aunoni" domin mutane su xauka har yanzu daular Sarkuna ake. Bature kuma da yake shi abin da ya kawo shi dabam ne, ba domin ci gaban qasar ba ne sai dai domin "me za su samu" a qasar, sai suka kau da kai akan abin da saraki masu mulki ke yiwa jama'a. Musamman wajen azabtarwa da sunan tara haraji, jangali da sauran kuxin Baitul-Mali, domin tafiyar da mulki da kuma biyan harajin mallaka ga gwamnatin Ingila.

"Babban abin da Bature ya kashe shi ne "bauta" na mallakar mutane a matsayin sashin dukiyar mai su. A maimakonsa sai aka qirqiro, "Aikin gayya na tilas" wai da sunan ci gaba. Aka kuma xora tara kamar su harajin numfashi ga namiji mai shekara 16 zuwa sama, ko yana da sana'a ko babu. Bugu da qari aka daxa zafafa hukunci, bisa laifi komai qanqantarsa, saboda talaka ya yi biyayya ga uwayen gidansa biyu. Wato tsohon Ubangijinsa "Sarki" da sabon dodonsa, "Bature."[1]

A duk lokacin da 'yan adawa da hamayya da Sarakuna za su bada labari sai su yi yadda za su baqanta Sarakuna. A kullum sai suce "Sarakuna na azabtarda talakawa", babu gaira ba sabab. Babu qashin gaskiya a wannan hasashe maras tushe. A qarqashin *Indirect Rule* kamar yadda Malam Sa'adu Zungur ne ya ce ne: "Ai Sarakuna kam hotuna ne", Saboda "Razdan, Di'o da su ADO, su ke da wuqa, su ke fidar mulkin jama'a bisa kan garari." To, idan haka ne ina laifin sarakai, waxanda aka ci da yaqi?

Amma maimakon ayi la'akari da irin muguwar siyasar dake qasa sai masu fafitikar neman qwatar mulki da sunan qwatar 'yanci daga Sarakuna, su yi amfani da wannan damar su muzanta Sarakuna, waxanda qaddara ta jefa su a tsaka mai wuya. Har yanzu suna nan da jihadin qwatar mulki a wannan lokaci da Sarakuna basu da ikon aiwata komai. Saboda haka ne kake jin hasashe mara kima kamar yadda Dr. Jumare ya yi kamar haka:

"Dukan irin wannan shimfixar tafiyar da rayuwar jama'a ana aiwatar da ita ne ta kan,"karnukan farauta", wato waxanda aka naxa a matsayin "Sarakuna", "Hakimai" da "Gororin Jama'a " ko kuma ace Dagaci da maroqa masu shela. Ganin Sarki da "salla" ko "Hawar Daushe" aka mayar da shi kamar ganin Allah ne wanda talakawa ke tilasta wa kansu wai domin ibada ce ta xebe zunubi. Shi kuma "Zaki", wato Bature, ganinsa kamar ace "Mutumin da ya mutu ne ya dawo", kamar ganin "fatalwa." Domin a qara qarfin mallaka aka kuma vullo da kuxin qasa domin tafiyar da hukuma, maimakon "kuxin Sarki" da da, irin su haraji,

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa* , shafi na . 301-302

jangali, moran qasa da dai sauransu. Aka kuma mai da harshen Turanci ya zama harshen kasa, maimakon harsunan jama'a da ake amfani da su."[1]

Irin waxannan kalamai marasa kyau ko tushen gaskiya 'yan NEPU ke furtawa daga wancan lokaci har ya zuwa yanzu. Domin rashin fahimtar "Mulkin Mallaka" da kuma kasa bambanta "Bature" da "Sarki." A wajen su Mulkin Mallaka da mulkin Sarakuna duk xaya suke saboda haka Sarki Bature ne Bature kuma Sarki ne. Tsarin mulkin wancan zamani ya juyar masu da qwaqwalwa ya kuma karkatar masu da tunani domin kada su sami mafita daga aqubar Mulkin Mallaka wadda manufarta, ta maida Arewa kidahuma. A wancan zamani 'yan NEPU sun xauka basillar xinke varakar al'amarinsu yana ga Ibo 'yan jami'yyar NCNC waxanda suke yin imani sune da ilmi da qwaqwalwar mulkin Nijeriya sune kuma za su iya fidda Arewa daga cikin"mulkin fitina da kisan Garari," idan wannan Jam'iyya ta kafa gwamnati a mulkin wannan qasa.

Saboda haka a maimakon su baiwa Sarakuna haxin kai a xauki gwagwarmayar darkake Mulkin Mallaka a cikin hankali da ilmi da dibara, sai 'yan NEPU suka haxa kai da qabilar Ibo domin su ci mutuncin Sarakunansu waxanda ke tsaka-mai-wuya. A ganinsu da tsageranci da qarfin tsiya za su kai ga nasara a yaqinsu na Neman Sawaba. Tun daga wancan lokaci har yazuwa yanzu masu wannan ra'ayi kullum a shirye suke su sayar da Arewa da jama'arta ga 'yan Kudu domin zakwaxin son quxi ko mulki. A dalilin haka ne Arewa ke dushewa matuqar dushewa saboda samun haxin kai ya faskara. Bugu da qari kuma su tsaya su yi nazarin kurakuran shugabannin wancan zamani domin fahimtar darussa masu amfani, sai suka qeqasa qasa suka qi. Saboda sun xauki waxannan shugabanni ma'asumai ne, komai suka yi dai-dai ne ba sa kuskure ko laifi.

'Yan adawa da gaba Sarakuna ra'ayinsu baya la'akari da zamani baya kuma sauyawa da zamani. Yau shekara kusan hamsin da samun 'yancin Nijeriya, amma har yanzu kusan yadda tsarin Mulkin Mallaka ya ke a Jihar Arewa a zamaninTurawa bai sauya ba. Haka kuma masu adawa da Sarakuna na tunanin har yanzu Arewa na karqashin *Indirect Rule* don haka suke zafafa qiyayyarsu da Sarakuna. Amma Sardauna Ahmadu ya nuna yadda siyasa zata tafi kafaxa da kafaxa da Sarakuna. Ya kuma aiwatar da wannan kyakkyawan shiri na Sarakuna a siyasa, wanda da shi ne Sardauna ya yi katafaren ayyukan da suka fidda Arewa daga aqubar Mulkin Mallaka. Firimiya ya sha faxi a bainar jama'a cewar abar yabonsa shi kaxai saboda da taimakon 'yan Majalisar Sarakuna da Majalisar Wakilai ne ya samu damar yin ayyuka masu yawan gaske, waxanda a yanzu muke cin amfaninsu.

---

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa*, shafi na . 307

A kullum shi kaxai ake yabo, A kullum Sarakuna ake zagi. Amma an ka sa samun wanda zai kamanta irin ta Sardauna saboda rashin tsari mai kyau. Da wuya a samu shugabanci mai kyau da adalci a Arewa sai Sarakuna sun shiga siyasa ka'in da nu'in. Domin da Sarakuna ne Sir Ahmadu Bello ya zama wani tauraro mai haske kuma abin misali a tarihin Nahiyar Afirka. Har ila yau ana iya yin kambunbaka da cewa Arewa ta tafi ke nan im babu Sarakuna a cikin harkokin mulkinta, ka'in da na'in.

Bugu da qari kuma qiyayya da Sarakuna ne ya haifar da tavarvArewar arziki, addini da siyasa a Arewa. Saboda abin takaici ne ganin yadda 'yan Arewa suka yi watsi da xabiu da al'adunsu suka rungumi na 'yan Kudu da sunan ci gaba da son zaman lafiya da gamuwar kai a komai da komai. A wannan lokaci ne ma har wasunsu ma suna "sabunta sahabbai" da 'yan Kudu saboda sune abin koyi da nuna misali ta hali da aiki a wannan zamani. A dalilin haka ana iya cewa Arewa ta fito daga mulkin mallakar Turawa ta kuma faxa cikin mulkin mallakar 'yan Kudu. Har ila yau a wannan zamani ne Arewa ke ganin mummunar tasirin jam'iyyar NCNC ta siyasar tsageranci da gaba da hamayya da Sarakuna.

A kuma irin wannan hali na yaqi da Sarakuna ido rufe, baki buxe da kunne rufe ne ya jefa Arewa cikin mugun matsayin da ta samu kanta na Mulkin Mallakar 'yan Kudu. Kowa yasan illolin da Daula Xaya Iko Uku ya haifar yake kuma haifarwa a Arewa. Masu ilimin Arewa sun fi kowa sanin haka. Alal misali, Dr. Jumare da ya yi nazarin wannan tsari cewa ya yi: "Al'ummar Nijeriya da suka saba da mulki kai fi xaya, sai ga su da uku. Ga Gwamna Janar, ga Firayim Minista ga Majalisar qasa. A jihohi waxanda a da sune iyakar daular mulkin kowace gwamnati, aka sa Gwamna, Firimiya, Majalisar Wakilai da Majalisar Sarakuna, maimakon abin da a da jama'a suka sani, Sultan da Majalisarsa kawai yanzu abin ya zama huxu.[1]amma kuma a lokacin da Sultan da Majalisarsa ke mulki ingantacce sai 'yan adawa suka bi shi da suka da qazafin danniya da rashawa da cin hanci. A dalili haka ne hatta kyautar Al'ada sai da suka haramta shi ballantana muxlaqin mulkin da suka yi wa sakiyar da babu ruwa.

Ya ci gaba da cewa: "Gwamna, Majalisar Sarakuna duk wasu abubuwa ne baqi. Kama ta ya yi ace an bar Firimiya, wanda shi wakili ne a Majalisar Wakilai tare da Wakilai, wanda shi zai zama ba a kauce daga al'ada ba."[2] A nan ma marubucin ya nuna gaba da Sarakuna domin bai ga amfanin Majalisar Sarakuna ba wadda kuma ta taka muhimmiyar rawa wajen yin ayyukan ci gaban kasa da kyautata jin daxin jama'a. Amma ya amince da mulkin Sultan da Majalisarsa. Sarkin Musulmi shi ne Sultan, Sarakuna kuma su ne 'yan Majalisarsa. Dalilin da ya bayar akan haka shi ne:

---

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa*, shafi na . 307

[2] *Ibid.*

"Lardi wani sabon abu ne da babu shi a cikin al'adar mulkin mutanen Nijeriya. Dalili kuwa shi ne a da babu wani lokacin da jama'a suka ga inda aka haxa Sarakuna biyu ko fiye da haka ana mulkin su, kuma ba su da ikon zuwa qololuwa, hedkwata . . . Shugabancin jama'a aka ruxa shi, ta yadda jama'a zai wuyan su gane babba a tsakanin Gwamna da Firimiya. Haka aka gwama Sarakuna da Razdan – Razdan da S.D.O – S.D.O., a qasashen Sarakuna. A gundumomi kuma aka haxa Hakimi da Di'o – Di'o. Tambaya a nan ita ce, wane ne shugaban, wanen mutane za su kalla ko kuma su saurara, ko zarga idan abubuwa sun vaci? Wannan irin tsarin, shi ne Bature ya sa masa suna"Rarraba-kai-a-Mulka."[1]

To, a cikin wannan kwamacalar da ta hargitsa tsarin mulki a Arewa wadda kuma nufinta shi ne a "Rarraba-kai-a-mulka" wanda da Turanci ana kiransa *Divide Et impera or Divide and Rule*, me ya sa aka dora vacin al'amura akan Sarakuna duk da an san cewar da qarfin igwa aka garqama masu *Indirect Rule*. Har yanzu da yawa daga cikin 'yan bokon Arewa suna nan da kiyayyar da aka cunkusa masu ta Sarakunansu tun daga zamanin COBA. Amma babu yadda qiyayya da Sarakuna zai taimaka wajen gyara al'amuran Arewa a yanzu. Abin da ya kamata mu yi shi ne muka wo qarshen illolin da Mulkin Mallaka ya haddasa mana. Kowace qasar Musulmi da ta samu 'yancin kanta sai da tayi nazari na musamman don ta gane abubuwa munana da ta gada daga Mulkin Mallaka. Ga wasu misalai:

Illa mafi muni da tasiri babu kamar wofintar da Makarantar Allo da Tsangayu dake birni da qauyen Arewa. Har yanzu ba a xauki ilimin Addinin Musulunci da muhimmanci ba saboda shi ne Turawa suka fara yi wa sakiyar da babu ruwa, a farkon shigowarsu Arewa a shekarar 1903. Gwamna Lugga bai vata lokaci ba wajen faxa wa shugabanninn hamvararriyar Daular Usumaniyya cewa babu ruwan gwamnatinsa da addini.[2] Saboda haka babu ruwansa da masu ilimi da shugabannin wannan addini. Wannan shi ne tarwatsa Makarantar Allo, ya kuma jefa miliyoyin almajirai da malamai cikin masifar hutunci da qasqanci a qasarsu ta haihuwa.

Harshen Turanci shi ne aka mayar harshen qasa, sauran harsunan qasar kuwa aka xauke su"yare." Dukan wasu hanyoyi na sana'ar jama'a aka maida su shirme aka kawo tsari mai shigen irin na Turawa. Abinci, hanyoyin sadarwa, tufafi da tsarin zama duka aka shiga canza su zuwa ga na Bature. Abubuwan jama'a bisa al'adunsu kuwa aka maida da su suka zama wai na "gargajiya" a

[1] GTK 8/2/1956.

[2] Abdulmaliku Mani, *Zuwan Turawa Nijeriya ta Arewa*, shafi na 124

domin haka ba su iya kawo ci gaban. Qarfi da yaji aka murqushe dukan al'adun jama'a, musamman ta fuskar sana'o'i, a maimakon a kyautata su a kuma inganta su domin su dace da hanyar sabuwar rayuwar jama'a, sai aka watsar da su .[1]"

Bugu da qari kuma aka cunkusawa masu ilimin zamani kiyayyar sarkauna d aMakarantun Allo duk da cewa an san amfaninsu wajen ci gaban Arewa. A fagen siyasa kuwa an bar Arewa da siyasa da gaba wadda take siyasa cewadda ta rarraba kan jama'a ta hanyar cunkusa masu munanan ra'ayoyi. Wannan balai ya haifar da rashin tasirin Arewa a harkar siyasa saboda an xauki 'yan Arewa taron tsintsiya ne shirim amma ba shara. Haka kuma Haxaxxiyar Arewa da aka gada daga mulkin su Sardauna wato *Monolithic North* an wargazata. A taqaice dai tsarin nan na rarraba-kai-a-mulka ya yi mugun raunana Arewa matuqar gaske, har ya maida 'yan Arewa bayi a qasar Nijeriya. Saboda rashin kishi da rashin sanin ciwon kai.

Har ila yau, ana iya cewa yanzu idan 'yan Arewa biyu suka haxu ba abin da suke tattaunawa sai yadda za su kassara na ukunsu. Saboda qiyayyar juna da haddasa sun yi masu katutu, talauci kuma ya mamaye su. A dalilin haka ne suka yi watsi da Aikin Tsaro (soja da xansanda) da Aikin kula da lafiya (likitoci da ma'aikatan jiyya) da Malaman Makaranta (Firamare zuwa jami'i). Saboda waxannan muhimman ayyukan jama'a na ga hannun maqiyansu ne shi ya sa aka xauki Arewa kida huma ce a wannan zamani. 'Yan Arewa kuma marasa kangado. Wata illa mummuna da mulkin mallaka ya haifar wa Arewa shi ne Siyasar qiyayya da tsageranci.

Siyasar Qiyayya da Tsageranci

Turawan Mulki sun yi amfani da *Indirect Rule* sun dagula siyasa a Arewa a bisa tsarinsu na Divide et impera. Saboda kafuwar siyasa da havakarta a Arewa za su kawo wa Turawa barin Nijeriya da gaggawa. Domin a kullum suna tsoron kada Arewa ta farka domin idan tafarka zata zama kamar qasar Indiya wadda ta yi gwagwarmayar qwatar 'yancin kanta ta kuma samu a shekarar 1947. Duk da haka sai da qasar Ingila ta yi kutingwilar raba qasar biyu Indiya da Pakistan.

Ko da yake ba a raba Jihar Arewa biyu ba amma Turawa sun kasata sashe-sashe kowane sashe na gaba da hamayya da wani sashe. A wannan lokaci Sarakuna ne garkuwa Turawa, tun da ta kansu ne ake mulkin jama'a. A shekarar shekarar 1934 guguwar siyasa tafara tasowa daga Kudu, a kuma wannan shekara ce Malam Sa'adu Zungur ya tafi kwalejin Yaba don qaro ilimi. Guguwar Siyasa sai ta taso da gwagwarmayar neman 'yancin kai daga Kudu. A wannan lokaci Turawa basu fara tunanin barin Nijeriya ba. Saboda haka sai suka xauki matakai

[1] Mohammed A. Jumare, *Rayuwar Talaka da Gwagwarmayarsa*, Ahmadu Bello University, Press Ltd. Zaria (2008), shafi na . 299-301

daban-daban domin ganin siyasa bata kafu a Arewa ba domin a dushe maganar neman 'yancin kai.

To, da jam'iyyu biyu, NPC da NEPU suka kafu amma bada son Turawa ba saboda haka sai suka sanya qiyayya da rashin jituwa a tsakaninsu. Jam'iyyar NEPU kamar reshen jam'iyyar NCNC ce a Arewa wadda ta yi baqin suna wajen siyasar tsageranci wato siyasar korar Turawa a Kudu da faxa da Sarakuna da Turawa a Arewa. Saboda fahimtar NEPU da NCNC na qut-da-qut da Turawa suka yi, sai suka labe da guzuma don su harbi karsana. Suka riqa muzgunawa 'yan NEPU amma takan Sarakuna. A dalilin haka ne sai Sarakuna kuma suka yi amfani da jam'iyyar NPC wajen biyan buqatunsu. Don kuwa an ce karen bana maganin zomon bana.

A wannan lokaci sai masu ilimin zamani suka yi amfani da rashin jituwar da ke akwai a tsakanin Sarakuna da talakawa, wajen qarfafa yaqin qwatar 'yancinsu daga Sarakuna. Sai suka riqa rura wutar qiyayya suna kuma tunzura talakawa don su yiwa Sarakuna bore ba domin komai don su samu karya lagon Sarakuna. Saboda haka sai aka wayi gari Turawa da Sarakuna na gefen NPC, talakawa da wasu zaratan masu ilimin zamani kuma na gefen NEPU.

Saboda haka a kullum sai kwarmato 'yan NEPU ke yi suna kukan zalunci da mulkin kamakaryan Sarakuna. Kada fa a manta Turawan Mulki ke gallazawa Talakawa aquba saboda tsoron kada siyasar NCNC ta yi tasiri a Arewa. Saboda wannan jam'iyya ce tafi zaqewa wajen neman korar Turawa a Nijeriya. Alhaji Bala Keffi wani sanannan xan NEPU a Kaduna ya bayyana abin da ke faruwa a wannan lokaci, inda ya ce:

"A lokacin qasar nan kaf ba mutum ne babu ba, talaka yana cikin tala kansa. Bashi da ikon komai, sai abin da aka ce ya yi bashi da cewa ko xaya. A lokacin abubuwa duk komai muninsu babu wanda ya isa ya yi magana akai. A lokacin ne Sarakuna da Alqalai, a taqaice dai wanda yake ma'aikaci daga kan Sarki zuwa masinja na N.A, sune waxanda suke masu sawa masu hanawa a qarqashin mulkin Turawa. . . A lokacin talaka bashi da ikon abin da zai yi sai abin da aka sa shi. In kuma aka aiko shi daga nan ko mil dubu ne a qasa zai tafi, ba za a bashi komai ba."[1]

Har yanzu talaka bashi da ikon yin komai sai abin da hukuma ta zartar bisa tsarin mulki da doka, Amma idan aka yi nazarin yadda al'amura suke a da za a fahimci yadda *Indiect Rule* ya haddasa tafka danniya da zalunci. Wannan mulki sai ya jefa Sarakuna a tsaka mai wuya, babu jin daxi wajen talakawa haka kuma babu jin daxin wajen masu ilimin zamani sai nadiran. Turawa basa son Sarakuna

[1] Ahmed Abdulqadir, *Gambo Sawaba*, shafi na 69 & 70

su sami goyon talakawa saboda suna tsoron kafuwa da yaxuwar siyasa musamman siyasar tsageranci wadda ita suke gani zata koresa a Nijeriya. Haka kuma masu ilimin zamani basa son Sarakuna su sami goyon bayan talakawa saboda yaqinsu na qwatar 'yanci, ya kai ga nasara.

Saboda haka ne sai rikice-rikice tsakanin NPC da NEPU suka turnike, magoya bayansu suka riqa karo-da-karo da juna. Ta haka ne aka janye hankalin jama'ar Arewa daga neman 'yancin kai har na tsawan wani lokaci. Wato *Divide et impera* ya taimaki Turawa ke nan, masu ilimin zamani kuma sun amfana da shi. Saboda rikicin NPC da NEPU ya taimaka gaya wajen zaizaye ikon Sarakuna a Arewa. Shi ne kuma yasa siyasar gaba da qiyayya ta hudo kai a Arewa.

Siyasa bata yiwuwa sai da adawa amma ba irin ta NEPU da NPC ba. Wadda bata amfani Sarakuna da talakawa ba. Waxanda suka amfana sune Turawa da 'yan Arewa masu ilimin zamani. Domin kuwa Turawa a fakaice ne suka yi amfani da NPC don su darkake NEPU wadda ita ce kaxai ke da ra'ain siyasar NCNC. A dalilin haka an xaure xaruruwan 'yan NEPU, xaruruwa kuma sun ga a quba iri-iri. A wata irin rikirkitacciyar siyasa wadda wani sashe ke karo da wani sashe. A wannan gwagwarmaya 'yan NEPU ne ke wahala domin kuwa ba yadda za su yi su karya Turawan Mulki. Domin suke mulki ta kan Sarakuna. A dalilin haka ne sai 'yan NEPU suka koma yin waqe waqen zambo da vata Sarakuna, a lokacin da suka yi watsi da sana'a da neman ilimi, a wajen yaqinsu na neman sawaba.

A irin wannan salon faxa da hukuma, Malam Sa'adu Zungur ya wallafa waqar Jihadin Neman Sawaba. A cikin wannan waqa ya bayyana irin taskun da talaka ke ciki. Ya ce:

An tal qahharu ka rinjaye su
Ka tilasta su a kan lamari

Ka tsare mu da makaru da mai sihiri
Da mawaqin 'yan gatan garari

Da ya rera jawabin alfahari
Wai talakka talolon masu gari

A aza masa kurxi don garari
Tilas ya biya ya kiyayi mari

Sarqa, gigar, ankwa da mari
Duk makamai ne na kisan garari
Mu biya gandu mu biya ushuri
Mu biya tara da shiga haxari.

Da kuxin lasin da kuxin ushuri
Mu biya tikitin mota a gari

Duk kuxin rumfar tallan mazari
Da dukkan hajja har mandawari

Da kuxin qarar dukkan lamari
A gaban Alqalin masu gari

A kama mutum ba gaira bare
Sababi da dalili sai fahari

In kayi afil ma kayi varin
Kurxin ka a tafqin 'yan garari.

Sun mai da talakka kamar dabba
Dokin sukuwar su na masu gari.[1]

Malam Sa'adu Zungur, a xunkule, a waxannan baitocin waqarsa ya bayyana mana irin aqubar da talaka ya samu kansa. Babu kuma yadda zai yi, ya fidda kansa, in ba bin hukuma ba. Amma yin haka a wancan zamani, ai kamar yin ridda ne ga 'yan wannan jam'iyya. Ko da yake an san da ilimi da sana'a ne ake qwatar 'yanci amma sai aka yi watsi da su a wannan yaqi. Saboda haka babu yadda za a yi Jihadin Neman Sawaba ya kai ga nasara Alhaji (Dr) Abubakar Imam ya fahimci cewa illolin *Indirect Rule* ya haddasa masifu a Arewa. Shi kuwa Malam Sa'adu, masifun ne ya gani sun rikirkita Arewa. Don haka ne ya ce:

Komai na Arewa da bambanci
Da na al'ummomi sun fi xari

Daularsu dabam, cinikinsu dabam
Iliminsu dabam don ba nazari

Daularsu kamar rigarsu take
Ga yawa ba amfani nagari
Cinikinsu kamar wadonsu yake
Bujensu da ba shi da alqadari

[1] A.M. Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na . 372 & 374

Iliminsu kamar rawaninsu yake
Xaure-xauren banza ba nazari.[1]

Wata qila, a nan Sa'adu yana nufin daular zamaninsa wadda Turawa suke mulki, ke da waxannan illoli munana. Domin a waqarsa Arewa Jamhuriya Ko Mulukiya, ya yabi Daular Usmaniya, ya kuma nuna faidodin Mulukiya ga Arewa. Amma a nan sai ya ce "komai na Arewa da bambanci, da na al'ummomi sun fi xari." Akwai qashin gaskiya a wannan hasashe. A zuwan Turawa ne duk al'amuranta suka birkice mata. Saboda Arewa ce jiha a wannan qasa wadda ta fuskanci illoli iri biyu a lokaci guda: illolin Mulkin Mallaka da illolin *Indirect Rule*. Illolin *Indirect Rule* ne suka birkitata har ta bambanta da sauran al'ummomi.

A cikin wannan waqar ya kawo kaxan daga cikin illolin Mulkin Mallaka wanda ya haifar da na *Indirect Rule*. Ya ce:

Mu Turawa ba mu burin
Dauwama a Arewa qasa ta gari

Mun shekara hamsin tare da ku
Saura saba'in bisa alqawari

Ku dai ku cika mana alqawari
Don Arewa ta rayu qasar garari

Ga qasarku qasa mai albarka
Ga salama babu yawan haxari

Kar ku yarda da 'yan Kudu arna ne
Za su gaje qasarku da al'amari

Za su gaje ayyuka masu yawa
Siniya sabis da na masu gari.[2]

Malam Sa'adu Zungur mashahurin mutum ne ya goge wajen siyasa ya kuma kutsa lungunan jihohin Gabas da Yamma. A zamaninsa babu wani xan Arewa wanda ya karanci 'yan Kudu, ya kuma fahimce su kamarsa. Har ila yau, Allah Ya bashi ilhamar hangen qarshen al'amari. Saboda so da kishin da yake wa Arewa ya

[1] A.M. Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na . 374

[2] *Ibid*.

fayyace mata komai dalla-dalla. Kusan duk abubuwan da ya faxi sun faru a wannan zamani. Wannan Gwarzo ya yi kira ga 'yan Arewa da kada su amincewa 'yan Kudu domin za su mallake su. Wato su lura kada mulkin 'yan Kudu ya maye gurbin mulkin Turawa. Idan haka ya fara, to, Arewa zata zama a qarqashin Mulkin Mallaka ke nan abadan sai inda masalaha ta tsaya! To, an ce dai, in kunne ya ji jiki ya tsira. Don kuwa ya gargaxi jama'arsa da gaskiya inda ya ce:

In kunka sake jama'ar Kudu
Suka hau mulkin Nijeriya

Daxa ba sauran mai tambaya
Kowa ya san zai sha wuya.[1]

A wannan lokaci yanzu ai 'yan Kudu ba gajen ayyuka kawai suka yi ba, a'a sun mallake Arewa ne baki xayanta, ta kuma kowanne fanni. Sun sami nasarar cimma nasara saboda rashin kishin Arewa da shugabanninta ke nuna wa da kuma qin xaukar gargaxin magabata kamar su M. Sa'adu Zungur.

A dalilin haka ne 'yan Arewa suka haxa kai da 'yan Kudu wajen kafa mulkin Jamhuriya.

Abin da basu sani ba shi ne a dai-dai lokacin da 'yan bokon Arewa suka dakata da yaqin Qwatar 'Yanci, a shekarar 1966 daga nan ne 'Yan Kudu suka xauki yaqin Martani Ga Daular Usmaniya. Ayya, ina ma 'yan Arewa sun ji gargadin "Kar ku yarda 'yan Kudu arna ne, za su gaje qasarku da al'amari!"

Akwai 'yan Arewa sahihai da suka yi wa 'yan Kudu kyakkyawar fahimta kamar M. Sa'adu Zungur, suka kuma yi mata gargaxi a lokacin da mulkin kansu, 'yan Kudu sun fitar da maitarsu a fili ta mallakar jihar Arewa. Sun ci duga-dugin Turawan mulki wajen neman samun 'yanci ba don komai ba sai don su mallake Arewa. Don haka ne ma ba su voye qiyayyarsu ga Sarakuna ba.

[1] A.M. Yakubu, *Sa'adu Zungur*, shafi na . 374

KASHI NA GOMA SHA-BAKWAI

Mulkin Kan Jihar Arewa

Farkon Sabon Yanayi

A shekarar 1958 ne Arewa ta shiga shirye-shiryen karvar mulkin kai daga qasar Ingila. A farkon wannan shekarar sai gwamnatin jiha ta fito fili da gagarumin shirin da ta yi don cimma wannan manufa. To, yaya matsayin Sarakuna zai kasance idan Arewa ta sami mulkin kai, a qarshen mulki ta kan Sarakuna? Wannan shi ne qalubale babba da ya fuskanci 'yan Siyasa, da gwamnati, da Sarakuna saboda an hangi cewa za a samu mulkin kai amma kuma babu haxin kai. Nijeriya ta Arewa zata shiga farkon sabon yanayi na gina sabuwar Arewa.

Gwamnan Jihar Arewa, Sir Gawain Bell ya yiwa Majalisar Wakilai jawabi a taronta na duba Istimat da ta buxe a ran 19 ga Fabrairun shekarar 1958. Kafin gwamnan ya yi jawabin, sai da ya duba faretin 'yan Sanda tukun, 'yan badujalan En'e ta Katsina su ne suka yi kaxe – kaxe da bushe-bushe. A wannan taron ne Gwamna Bell, ya ce: "Gwamnati tana ganin yanzu lokaci ya yi, don haka tana da niyyar kawo wani batu gaban majalisan nan, bisa roqon Mai Alfarma Sarauniya ta yarda, cikin karimcin nan ta tabbatar da Mulkin Kai ga jama'ar Jihar Arewa, waxanda ba su da na biyu wajen biyayya gare ta, a ran 15 ga watan Maris na 1959." [1]

To, da wane buri gwamnatin Sardauna take neman wannan mulkin kai? Ga amsarsa: "Burinmu, kamar yadda burin kowace gwamnati ta mahankalta take, ita ce ko ada, ko da yanzu, ta kula da tsare asiri, zaman lafiya, walwalar jama'a, da qara ci gabansu. Don su sami kaiwa ga haka nan, shi ya sa muka qarfafa maganar sha'anin ilimi, tun ma ba na makarantun sana'o'i ba, inda ba za a buqaci zurzurfan ilimi ba, saboda qara shigowa da sana'o'i iri-iri da aka ya."[2] Firimiya zai shigar da Arewa cikin sabon falle na tarihi da kyakkyawar niyya.

Domin kuwa ko shakka babu wannan gwamnati ce ta mahankalta wadda take da kyakkyawan buri ga jama'arta. Tana kuma yin ayyukanta bisa tsari da hankali. Saboda haka ne ma tun a shekarar 1952, Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato, ke faxi yana kuma nanatawa: "A zamanin nan na yau, ba mu son nawa, ba mu son saurin da zai haifi nawa." Saboda haka a bisa kan ilimi da sana'a, gwamnatinsa ta

---

[1] GTK 21/2/1958

[2] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 218

xora harsashin mulkin kai, wato a kan aqidar yaxa ilimi, yaqi da cin hanci da Siyasa da Sarakuna. A dalilin haka ne Sardauna ya ce: "Kuma in ba a tasamma jahilci gadan-gadan ba, jama'armu ba za su iya bimmu a tafiyan nan da mu ke yi a gurjuje ba, bisa tafarkin ci gaban qasan nan. Wannan yaqi kuwa da za a aukawa jahilci, zai haxa har da yaqi da cin rashawa, a kuma kyautata Majalisun En'e En'e don su dace da zamani."[1]

Ita wannan gwamnati burin ta ne ta gina matasa ta Aiki da Ibada ta kuma sa ido a kan ganin sun zama kyawawan tubalan ginin al'ummarsu masu kuma qarfi da qarko waxanda za su iya fuskantar qalubalen kowane qarni a rayuwarsu. Amma matasa kaxai ba za su cimma wannan manufa ba sai da gudun mawar dattawansu. A dalilin haka ne Sardauna ya yi nuni da cewa: "Mai quruciyar da ba a kwava, sai a barshi ya yi abin da ya ga dama, kuma ba a sukar ra'ayinsa, sai ya zama xan shagwava raunananne." [2] Amma kusantowar mulki kai, ya zo da nasa qalubalen, musamman ta wajen dangatakar Sarakuna da 'Yan Siyasa.

Duk da xasawar da NPC da Sarakuna ke yi a wancan zamani, sai shugabannin wannan jam'iyya, suka lura da cewa sassaucin da suke wa Sarakuna zai haddasa matsala babba in har ba a yiwa tufka hanci ba. Wata qila ma wasu su xauka jam'iyyar ce ta xaure masu gindi don su ci gaba da tafka rashawa, wani abun da gwamnatin jiha ba ta lamuncewa ba. Ko da yake ance da bazar Sarakuna jam'iyyar NPC ke taka rawarta da kuma taimakon su ne ta kai ga cin nasarorin zavukan da aka yi. Duk da haka a shekarar 1958, sai da Firimiya, Sir Ahmadu Bello ya fito fili, ya kawo batun samun Mulkin Kan Arewa, a lokacin wani zama da ya yi da Majalisar Sarakuna.

A wannan zama ne ya sami damar nuna wa Sarakuna cewa im fa kixa ya sauya tilas rawa ma ta sauya. A wannan lokaci ne ya gargaxi shugabannin En'e, kamar haka: "Ina so in aika da wannan saqo ga shugabannin En'e da cewa samun Mulkin kai fa, na nufin Ma'aikatan En'e da su qara himmatuwa ne da himmar qara xaukar qarin nauyi da zai rataya a wuyansu. Amma mai yiwuwa wasu daga cikinsu, za su so bin hanyarsu ba ta gwamnatin jiha ba. In akwai masu wannan shucin gizo, ina so, yanzun nan in kore masu da cewa wannan ba zai savu ba, in kuma gargadi da mai tababa da yin haka. Ina so a san gwamnatin jiha ke riqe da ragamar mulki, za ta kuma ci gaba da riqe wannan ragamar… Na xauki wannan magana da zafi sosai. Ina kuma qara tabbatar maku da cewa gwamnati ta yi niyyar

---

[1] Ahmadu Bello, *Rayuwata*, shafi na 218

[2] *Ibid*. shafi na 221

mulkin wannan jiha, ke kuma kowanne mahaluki ya yi wani tunani da zai kaucewa wannan shirin.[1]"

Qaratowar mulkin kai, ya qara wa masu azamar qwatar 'yanci daga muxlaqin Mulki don haka fa sai aka assasa zargin da ake wa En'e da cin hanci da rashawa. Aka kuma yi qorafin cewa gwamnatin Ingilishi mai baringado ce ta sangartasu. Ana kuma raxeraxin cewa idan jam'iyyar NPC ba ta yi hankali ba, za a shafa mata kashin kaji. Saboda shugabannin En'e za su nemi su miqe qafafuwansu, su yi yadda suke so idan NPC ta karvi mulkin Arewa. Saboda haka lokaci ya yi da za a nuna wa waxannan shugabanni gwamnati jiha ke riqe da ragamar mulki ba wa 'yansu jama'a ba. A wannan gwamnati, tilas a ba da bayani akan komai, don kuwa wannan jami'yya ba za ta yarda da aiki ba bisa doka ko tsari ba. Ya kamata a fahimci wannan gwamnati tun yanzu domin kara yana xanye ake lanqwasa shi.

Idan har ba a tsawata a yanzu ba, to, shugabannin En'e za su sangarce, har su nemi su ci karensu babu babbaka. Idan gwamnatin jiha na so ta qara kwarjini da karvuwa ga jama'a, to, tilas ta nuna wa shugabannin En'e matsayinsu. A wannan lokaci sai siyasar nuna iko da mulki ta tashi haiqan, aka kuma qara baqanta mulkin En'e da laifukan rashawa da almubazziranci. Don haka ne a wannan lokaci, jam'iyyar NPC ta fito ta ja kunnen shugabannin En'e.

Arewa ta samu Mulkin kai, amma babu haxin kai, saboda ana takon-saqa tsakanin Sarakuna da Ministocin Arewa. Ko da yake tsarin mulki, doka ta nuna Ministoci Wakilai ne na Sarakuna, amma ba sa nuna haka a zahiri. Qoqarin maida Sarakuna qarqashin ikon Ministoci yaci tura har na tsawon lokaci wanda ya haifar da tavarbarewar dangantaka tsakaninsu. A farkon shekarar 1955, Sarakuna sun yi qorafin 'yan siyasa ba sa tuntuvar su wajen zartar da wasu hukunce-hukunce. Misali, ba a nemi shawarsu ba lokacin da su ka yi wa Ministoci qarin albashi da kashi hamsin bisa xari, daga fam dubu biyu (£2,000) zuwa fam dubu uku (£3,000) a shekara, da kuma fam xari huxu (£400) kuxin alawus, ban da albashin Firimiya da ya qaru daga fam dubu uku (£3,000) zuwa fam dubu huxu (£4,000) a shekara da fam xari shida (£600) kuxin alawus. Amma abin takaici Sarakuna da suke Ministoci marasa muqami (without Portfolio) sun sami qarin albashi ne daga fam xari uku da hamsin (£350) zuwa fam dubu xaya da xari shida da hamsin (£1,650) a shekara da kuxin alawus fam xari da hamsin (£3150) ne kawai.[2]

Irin wannan qoqarin maida Sarakuna qarqashin Ikon Ministoci, ba an yi shi ba ne don son ci gaban Arewa, halin 'yan siyasa ne ya fara fitowa fili wajen nuna son kansu tare da zalamar son mulki. Wannan hali ya raba kan shugabannin Arewa, musamman idan aka yi la'akari da qoqarin da 'yan siyasa su ke yi wajen vata

---

1 HCD, Tuesday 12/7/1958, shafi na 81

2 CO554/1183/143917: Report by the Governor, *Northern Region of Nigeria, to the Secretary of State for the Colonies, Secret and Personal*, 5, April, 1955, para. 8

Sarakuna, da rashawa, da murxiya da cin hanci. An ce laifi tudu ne sai ka tsallake naka kafin ka hango na wani. Saboda haka ne irin wannan hali na babakere da handama da 'yan siyasa ke nuna wa, sai ya kusa ya raba kan 'yan Majalisar Wakilai da 'yan Majalisar Sarakuna. Wannan hali ya haifar da rashin jituwa a tsakanin Sarakuna masu riqe da muqamin Ministoci da sauran Sarakuna a Majalisarsu, wadda ta kai har sun yi furucin yin murabus, saboda sun ce Gwamnati na zartar da hukunci gwamnati ba tare da an shawarce su ba.[1]

Wata qila wannan zaman doya da manja da 'yan Majalisar Sarakuna da 'yan Majalisar Wakilai ke yi, ba zai rasa nasaba da shirin *Divide et impera* da gwamnatin Mulki ke yi ba, amma duk da haka gwamnan Arewa Sir Sharwood-Smith ya tsawata akan tavarvArewar dangantaka a tsakanin waxannan Majalisun; ya ja kunnen qoqarin da Ministoci ke yi na maida Sarakuna qarqashinsu, da kuma zalamar su ta amfani da muqami don tara abin duniya, tare da zakwaxin son motoci da kuma amfani da duk wata dama wajen amfanin kawunansu.[2] Da haka Arewa ta kai ga samun mulkin kanta.

Alokacin da aka samu mulkin kai, kan shugabannin Arewa a rarrabe yake. Saboda hamayyar da ke akwai a tsakanin Sarakuna da 'yan siyasa. Shashe na zargin shashe da son kai da son nuna isa tare da tara abin duniya. Rabuwa sai ta shiga cikin 'yan Majalisun nan guda biyu, kishin Arewa da qoqarin yin hovvasa wajen fitar da Arewa daga matsalolin da suka kewata sai ya ragu sosai. Amma duk haka an sami Mulkin kai a 15 ga Maris xin shekarar 1959. A wannan ranar bikin samun Mulkin kai ne, Firimiya ya yi wannan jawabi, a *Lugard Hall*, a ranar 15 ga watan Maris xin shekarar 1959:

> *Gaisuwa ga Sarakunan qasar Ingila,*
>
> *Kamar shekaru uku da suka gabata al'umman Jihar Arewacin Nijeriya sun karvi baquncin Mai daraja Sarauniya Elzabet da kuma na mijinta Mai martaba Duke na Edingurgh sa'ilin da suka ziyarci wannan Jihar, a watan Fabrairun shekarar 1956, har masuka kai ziyara birnin Kano.*
>
> *A wannan lokacin mun gwadawa Mai daraja Sarauniya cewa babu wata qasa a cikin rukunin qasashen Commonwealth da Ingila ta rena wacce ta fi ta mu yin ladabi da biyayya ga uwargidanmu Sarauniyar Ingila, mu ne kuma kan gaba wajen mutunta ta da kuma darjanta ta.*
>
> *A yau ina so, a madadin xaukacin al'umman Arewacin Nijeriya, in nuna godiyarmu ga Maidaraja Sarauniya Elizabeth saboda saqon*

---

[1] HCD, Tuesday 12/7/1958, shafi na 81

[2] *Ibid*.

fatar alherin da ta aiko mana da shi don taya mu murnar zuwan wannan rana ta samun 'yancin Arewacin Nijeriya, ina kuma son in qara da cewa mun gamsu da irin fahimtar da ta yi na ci gaban da Jiharmu ta samu da kuma kasancewar al'ummanta cikin walwala da farin ciki.

Ina kuma so, a madadin xaukacin al'umman Arewacin Qasar nan in yi kyakkyawar marhabin ga babbar baquwarmu da mijinta, ba domin kasancewarta wakiliyar Maidaraja Sarauniya Elzabet ba, har ma da zamantowarta manyan baqin da suka ziyarce mu ita da mijinta. Wannan rana muhimmiya ce a gare mu, kuma muna murna da zuwanku don taya mu murnan zuwanta domin kuwa mai tarihi ce a gare mu.

To, ko da yake na ce maqasudin taruwarmu a nan a yau shi ne don murnar isowar ranar baiwa Arewacin Nijeriya 'yancinta, ba makawa samun 'yanci irin wannan babban al'amari ne ainun a rayuwar al'umma, kuma wajibi ne a yanzu in yi tsokaci da jan aikin da ke gabanmu don cin moriyar wannan 'yancin, ba wai kawai mu nutse cikin sharholiya da murnar zagayowar wannan ranar samun 'yancin ba kaxai.

Kamar sauran qasashen duniya yau ga 'yan Arewacin Nijeriya tsaye bisa dandamalin zauren shiga gidan da za su gudanar da ayyukansu don gina qasa, domin kuwa har yanzu ba su kai ko'ina ba a faxi-tashinsu na havaka tattalin arziqinsu da kuma cetar da al'ummarsu daga illolin jahilci da cututtukan da ke tauye su, suna hana su ci gaba.

Sa'ilin da nake juyayi game da ximbin matsalolin da suka dabaibaye mu, kamar yadda na kan yi a koda yaushe, cike da tunanin hanyoyin jawo hankalin jama'a don a tafi tare da su, sai kawai in yi ta tunawa da yadda tsohon Firayim Ministan Birtaniyya, Sir Winston Churchill ya sha yin fafitikar qarfafa zukatan al'ummar qasarsa, kamar shekaru goma sha-tara da suka shuxe, ta hanyar gaya masu gaskiya game da al'amuran da ke wanzuwa a wancan lokacin don su kasance masu qwazo da kuma qarfin hali da nuna tsananin kishin qasa da goyon bayan shugabanninsu don a samu nasara a yaqin duniya na biyu, wato yaqin Hitler.

Mu dai a nan Nijeriya shekarun shekarar 1959 da kuma ta 1960 suna da muhimmanci a gare mu kamar yadda shekarar 1940 ke da muhimmanci ga qasar Birtaniyya, kuma hakan ya nuna mana cewa muddin mu ma muna son kai wa ga nasara to fa wajibi mu kasance masu juriya da dauriya da sadaukar da kai domin kuwa waxannan ne

suka sanya qasashen da ke da 'yanci samun sukunin kaiwa ga biyan dukkan buqatunsu.

Idan Allah Ya kai mu baxi, wato shekarar 1960, za a fara aiki da yarjejeniyar da aka cimma a taron ayyanawa qasar nan kundin tsarin mulkin da zai ba ta dammar yin kafaxa da kafaxa da 'yantattun qasashen da ke cikin qungiyar qasashen da Ingila ta raina, wacce ake kira commonwealth. Idan har hakan ta faru, za mu yi alfaharin jerawa tare da manyan qasashen da suka shahara duniya, waxanda kuma wakilai ne a waccan qungiyar ta commonwealth, mu kuma yi alfahari da irin taimako da gudunmawar da suke ba mu.

Mun tabbatar da cewa idan mun nemi taimakonsu za mu samu a matsayinsu na abokan tafiyarmu ba tare da an xauke mu tamkar maroqa ba a cikin qungiyar domin mu ma akwai irin tamu gudunmawa da taimakon da za mu iya bayarwa saboda dai al'amarin zamantakewa cuxe-ni-in-cuxe-ka ne.

Amma game da batun da nake yi na gudunmawar ga wannan qungiya ta commonwealth idan Allah Ya kai mu shiga cikinta, walau ta hanyar kayan aiki ne ko qarfafa gwiwan juna, zan tsaya ne kawai kan 'yancin Arewacin Nijeriya, amma kuma dangane da haka wajibi ne in nuna cewa kodayake dai Jihar Arewa ita ce mafi girma daga cikin jihohi uku na tarayyar Nijeriya, duk da haka nan dai ta kasancewani vangare ne na Tarayyar Nijeriya. Amma kafin in ci gaba ya kamata in yi tanbihi game da wani abin da aka rigaya aka sani. Jihar Arewacin Nijeriya, mai yawan jama'a fiye da miliyan goma sha-takwas, ita ce ta biyu a nahiyar Afrika baya ga qasar Masar a yawan jama'a. Haka nan kuma ta fannin aikin gona Arewacin Nijeriya ce ta biyu a noman gyaxa a duniya, kuma Arewar ce xin dai ke samar da yawancin audugar da ake amfani da ita a Lancashier, wato garin da ya fi kowanne yawan masaqu a qasar Ingila.

Idan kuma aka koma kan batun haqo ma'adinai mun zarce kowa wajen samar da columbite, kuma qasashen duniya sun dogara ne ga kuzan da ake haqowa a Arewacin Nijeriya. Ta fannin masana'antu kuwa ana iya cewa a yanzu ne Arewacin Nijeriyake tasowa, amma gagarumar nasarar da aka samu wajen kafa masaqar Kaduna, wanda ba kamarta a girma a xaukacin nahiyar Yammacin Afrika, ya nuna ke nan cewa idan aka kammala aikin samar da wutar lantarki mai sauqi da araha ta hanyar datse kogin Kwara a Ka'inji nan gaba kaxan, za a samu sukunin kakkafa masana'antun da aka yi niyyar samarwa a wuraren da aka wawware a manyan biranen Arewacin Nijeriya don kakkafa masana'antu.

Yanzu kusan shekaru hamsin ke nan da muka fara hulxa da sauran qasashen duniya bayan zuwan dogon jirgin birnin Kano. Ashe ke nan muna iya bugun qirji mu cewaxannan nasarori ne da aka samu cikin shekaru hamsin da wanzuwar Nijeriya, kuma ana iya cewa wannan gajeren zamani ne a tarihin rayuwar wannan qasa.

Mu dai mun san yankin Arewacin Nijeriya ya kasance wuri ne da abokan tafiyarmu suka mayarwa kasuwar sayar da kayayyaki da hajojinsu. Bugu da qari kuma za mu samar da yanayin da zai kwantar da hankulan masu hulxar cinikayya da mu, mu kuma tsara hanyar yin haka bisa adalci da sanin ya kamata domin mun fi kowa xaukarta da ganin cewa harkokin cinikayya da kasuwanci da kuma zuba jari a wannan nahiya sun kankama. Waxannan su ne abubuwan da muka fi xauka da muhimmanci.

Na yi cikakken bayani game da harkokin kasuwanci saboda muhimmancinsa ga ci gaban wannan yankin da qaruwar arziqin al'umman cikinsa, kamar dai yadda hakan ke wanzuwa a qasar Ingila, kuma wannan ya dogara ne ga qoqari da qwazonmu na ci gaba da bin hanyar mu'amala da abokan cinikayyarmu da kuma inganta dabarunmu na yin kasuwanci da sauran qasashen duniya. Haka nan kuma bai kamata ba a ce sha'awar da muke da ita na kasancewa cikin qungiyar commonwealth don amfanin da za mu samu ne kawai daga gare ta idan Nijeriya ta kasancewakiliya a ciki. A zahiri abin da ya sa Arewacin Nijeriyake sha'awar Nijeriya zama wakiliyar qungiyar Commonwealth shi ne don qarfafa danqon zumuncin da ke wakana tsakanin wakilan qungiyar.

A duniyar wannan zamanin da al'ummomin cikinta suka rarrabu saboda abin duniya, sai ga shi nan qungiyar commonwealth ta kasance tsintsiya mai maxauri guda, wacce ta rungumi dukkan qasashen da ke cikinta ba tare da la'akari da bambancin jinsi, launin fata ko addini ba, kuma hakan ne ya sa ta yi fice cikin sauran qungiyoyin, kuma al'amuranta na ta qara gaba-gaba kamar qwaryar roro.

Haka nan ma kabilun wannan jiha ta Arewacin Nijeriya, waxanda harsuna, da addinansu suka sha bamban da na juna sai ga shi nan cikin xan qanqanen lokaci sun rugumi junansu, su zame xaya, ba tare da la'akari da irin banbamcin da suke da shi ba na qabilanci, yare da addini, suna kuma mutunta juna da girmama xabi'u da al'adunsu da kuma kare hakkin abokan zamansu.

Wannan mataki da muka xauka, wanda kuma ya nuna cewa mun yi imani da hukuncin Mahallici Allah na tattara mu wuri guda, shi ne

ke qara qarfafa mana gwiwa cewa idan lokaci ya zo, to a matsayinmu na wata jiha a tarayyar Nijeriya, za mu qoqarta wajen taimakawa Nijeriya ta kasancewakiliya a qungiyar Commonwealth duk kuwa da cewa za ta zame 'yar jaririya ce a cikin wannan qungiyar. Za mu kuma yi tsayuwa irin ta mai daka don ganin Nijeriya ta bayar da cikakkiyar gudunmawa don tabbatar da nasarar quingiyar Commonwealth.

Ya ku manyan baqinmu, daga fadar Maidaraja Sarauniyar Ingila, ina qara yi maku marhaban lale da zuwanku Arewacin Nijeriya. Arewacin Nijeriya dai wuri mai cike da xaxaxxun al'adun gargajiya, waxanda muke aiki da su don fahimtar al'adu da xabi'o'i irin na zamani. Za mu ci gaba da bin al'adumnu na gargajiya, da kuma gwama wasu daga cikinsu da al'adun Turawa idan akwai buqatar yin haka don mu tafi tare da zamani.

Daga cikin xabi'un da muka koya daga kaka-da-kakanninmu, wanda kuma muka riqe tamau don mu ma nan gaba mu koya wa na bayanmu, ba wanda ya wuce biyayyar da ta wajaba a yi wa hukumomi, shugabanni da kuma na gaba. Saboda yadda mutanenmu ke ganin girman mahukunta mun tabbata cewa nan gaba, kamar yadda magabatanmu suka yi, za a samu nasarar kawo zaman lafiya da lumana ta hanyar bin qa'idojin da hukumomi ke gindayawa.

Al'adu da gidajen sarautunmu ba abin wasa ne a gare mu ba, kuma ba wai aro irin tsarinsu aka yi ba daga wasu. Hasali ma saboda ganin yadda suka karvu ga al'ummomin da suka daxe da shuxewa, kuma har yanzu suna da mamora ga al'ummar yanzu, shi ya sa suka ci gaba da wanzuwa, ba wanda ya kawar da su. Muna alfahari da rayuwarmu bisa qa'idojin addininmu a matsayinmu na al'umman Arewacin Nijeriya, kuma ba ma jin kunyar nuna cewa ga yadda muke ga sauran al'ummomin duniya gaba xaya. Muna alfaharin cewa a yau za mu gwada maku kyawawan al'adunmu don ku gani ku kuma yaba qwarai. Muna fata za ku gamsu da abin da za ku kalla, kuma idan an qare bukukuwan samun 'yancin kai, Allah Maxaukakin Sarki Zai mayar da ku gida lafiya. Muna fatan Allah Ya ja zamanin Sarauniya Elzabet, Ya kuma ba ta ikon sake kawo mana ziyara nan ba da jimawa ba.

Ko da Arewa ta samu mulkin kai, amma ba ta da kyakkyawan haxin kan shugabanninta saboda haka ta riqa tafiya a shagixe, har sojoji suka yi juyin mulki a shekarar 1966. Wata qila, da ace an sami kyakkyawar jituwa tsakanin 'yan siyasa da Sarakuna, sun kuma haxa kai sosai, da wannan mummunan juyin mulki

bai wa Arewa, lahani mai muni ba. Tun daga shekarar 1966 har yanzu Arewa sai koma wa baya take yi, abin gwanin ban takaici. Matsayin Sarakuna kuma ya shiga tavarvarewa da hanzari. Bayan shekara goma da angije Siyasar farko sai gwamnatin Mulkin Soja qarqashin Janar Olusegun Obasanjo shekarar 1976 ta rage wa Sarakuna mulki a wani sabon shirin Qaramar Hukumomi. A taqaicewannan shiri ne ya kawo qarshen yaqin qwatan 'yanci da aka xauki kusan shekara arba'in ana yi. Shekarar 1959 ta zo wa Arewa cikin farin ciki saboda kyakkyawar shirin da jihar ta yi wa karvar mulkin kai. Saboda haka aka shirya yin shagulgula masu qayatarwa.

Shagulgulan Samun Mulkin Kai

Gidan Gwamnati wato State House da ke Kaduna na xaya daga cikin manyan wurare da za a yi bukukuwa a watan Mayu na shekarar 1959, saboda haka sai aka ba da kwangilar gina shi ga kamfanin D'Alberto, wanda ya yi suna wajen gine-gine a Kaduna. Kamfanin kuma ya gama aikinsa cikin gaggawa. Shugaban kwamitocin shirye-shiryen wannan qasaitaccen biki kuma jagoran shagulgulan Dabar, Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu ya sa ido sosai don ganin an kammala bikin ba tare da vata lokaci ba.

Haka kuma saboda muhimmancin aikin Gidan Gwamnati, ya sa Firayim Ministan Nijeriya Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa ya kawo ziyara Kaduna don ya gane wa idonsa yadda ayyukan shirye-shiryen bikin ke tafiya. A ranar Talata 5 ga Maris na shekarar 1959, Sir Ahmadu Bello ya jagoranci Wazirin Nijeriya da ayarinsa zuwa inda ake gina Gidan Gwamnati don yaga inda aiki ya kai. Shugaban kamfanin da ke kwangilar wannan gini Mr D. Alberto ya zagaya da su sassan wannan gini wanda aka yi shi da kyau da qarko kuma a cikin lokaci. Ana jin kuma a ran 9 ga Mayu duk an kammala wannan gini manyan baqin da suka ziyarci ginin sun gamsu qwarai da gaske, saboda an yi ginin da ba tare da amaja ba.

Duk titunan da za su kai ga wannan gida, an dave su da kwalta an kuma qawata su da filawoyi. Ayyukan lantarki da famfo da sauransu duk an kammalasu. Kamfanin D'Alberto and Bogialla Ltd., sun himmatu qwarai da gaske don a gama aikin cikin lokaci. Saboda haka ne suka zuba ma'aikata iri-iri wajen xari huxu, waxanda suka duqufa wajen aiki wurjajan. A dalilin haka ne babu wani aiki da ya yi saura a ran 9 ga Mayu, sai gwaje-gwajen da ma'aikatan P and T suke yi don tabbatar da telifon da aka sa a xakuna da ofisoshi suna aiki sosai kamar yadda ake buqata.[1]

A kusa da wannan gidan mulki kuwa har an kammala gina Qofar Mulkin Kai wato *Self-Government Arch*, wadda ta qawata babban titin da ke zuwa Gidan

[1] *Nigerian Citizen*, Asabar, May 9, (1959), shafi na 8

Gwamnati. Shagulgulan mulkin kan Arewa da za a a yi, ya fi kowane da aka tava yi. Da farko dai a jajibarin mulkin kai wato ranar Asabar, 14 ga Maris xin shekarar 1959, za a yi Wasan Wuta a filin sukuwa na Kaduna. Za a nuna hotunan Mai martaba Sarauniya da na Mai girma Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato. Babbar ranar kanta wato ran Lahadi 15 ga Mayu za a yi wani shagali a Lugar Hall, wanda zai nuna mutanen Jihar nan sun sami 'yancin kansu.

Saboda watan azumin Ramadan ya faxa a ainihin ranar mulkin kai, 15 ga Maris saboda haka dukkan manyan bukukuwa za a yi daga 14 zuwa 19 ga Mayu ne. Daga cikin shagulgulan da za a yi ba kamar hawan Dabar, wanda ake zaton zai fi wanda aka tava yi a da. Hawan Dabar wani irin shagali ne na 'yan Sarautan Indiya wanda mutane da masu dawakai dubbai su ke yin jafi. A riqa kewayawa har a haxu da babbar qungiya. (Abin da aka saba gani a Arewa ke nan, musamamman a qarshen watan Ramadan).[1]

Qasaitacciyar Daba

A shekarar 1956, aka yaba wa Jihar Arewa saboda iya kiwanta dawakai, lokacin da aka-yi qasaitaccen hawan Dabar, saboda ziyarar Sarauniya da mijinta Duke of Edinburgh. Amma hawan Dabar na watan Mayu na shekarar 1959 za ta doke ta 1956.

Ko da yake an sami watani masu yawa ana shirye-shirye, don a yi qasaitaccen bikin da aka gayyato baqi daga sassan duniya duka. A wannan shiri ne aka kafa runfunan kallon hawan Dabar da masaukin jama'a da na masu hawan Dabar. A filin sukuwa na Kaduna dai za a yi hawan Dabar. Kafin dai makon bukukuwan ya zo, za a gina runfunan masu abinci da za su xauki mutane dubu uku da xari biyar (3,500) da kuma tudun tsayuwar mutane dubu goma (10,000), inda mutane za su tsaya su yi kallon hawan Daba, da kuma sauran falalen fili saboda sauran mutane. Za a sami wani kevantaccen wuri don qungiyoyin samari.

Yawancin ministocin Jiha a qalla waxanda aka xora musu aikin yi suna zaune a Nasarawa ne (unguwar Ministoci). A bayan gidajen su, da xan tazara kaxan, nan za a yi qauyen Dabar, wanda faxinsa zai kai mil guda ta kowace fuska. Wurin zai xauki mutune dubu takwas (8,000) da dawakai dubu uku (3,000). Tushen runfunan da za a yi duk na qarfe ne.

Za a kafa tankin ruwa mai xaukar galan dubu hamsin (50,000), a gina hanyoyi, da wuraren tsayuwan 'yan Sanda, da malaman kula da dabbobi, da wurin jiyya da sauransu. An yi shirin yadda za a sami abincin dawakai, da isasshen ruwan sha. Alal misali, galan dubu tamanin (80,000) na ruwa za a tura saboda

[1] GTK, 19/12/1958, shafi na 7

amfanin mutane, da kuma galan dubu arba'in (40,000) daga kogin Kaduna don amfanin dawakai kowace rana.

Mr. R.N Jacobsen shi ne kwamandan sansanin Dabar, ya kuma bayyana cewa akwai mutane wajen dubu goma da xari bakwai (10,700) da dawakai dubu uku (3,000) a wannan sansani da ke da faxin eka xari uku da sittin da kuma mil huxu na hanyoyi masu kwalta. A kwai 'yan 'xakuna da aka yi da karfe masu rufin kwano da kuma xakunan zana masu yawan gaske. An kuma kafa famfuna da lantarki a kowane sashe na wannan fili. Haka kuma akwai xakunan zana wajen dubu talatin(30,000). An yi asibitin dabbobi da mayanka da wuraren wanka da shaddodi masu yawa a wannan fili. Ma'aikatar Kashe Wuta da ofishin 'yan Sanda duk an tanadar masu wurarensu. Kamfanin manfetur na Mobil Oil ya buxe gidan mai sa'an nan kamfanin U.A.C ya buxe kantin saye-saye.[1] Saboda haka an tanadi komai da komai wajen kula da lafiyar jama'a sosai da sosai.

An tanadi ton dubu maitan da hamsin (250,000) na hatsi da shanu xari uku da hamsin (350) don ciyar da dubban jama'ar da za su halarci wasan Dabar a wannan qasaitaccen bikin murnar samun Mulkin Kai.

Shugaban Majalisar Sansanin Shagulgulan bikin samun Mulkin kai shi ne Mai girma Sarkin Katsina Alhaji Sir Usman Nagogo, da mataimakinsa Ministan Lafiya na Jihar Arewa, Alhaji Ahman, Galadiman Pategi.[2] Dukkansu sun yi aiki tuquru wajen ganin bukuku wa da shagulgulan sun ta fi kamar yadda aka shirya ba tare da miskila ba.

Saboda dubban mutanen da suka halarci wannan biki sun kasance cikin farin ciki da annashuwa, a wannan lokaci sai amon waqe-waqe da kaxe-kaxen mawaqan Arewa ake ji a ko'ina ta na'urarin qara sauti da ke kafe a sassa da dama a wannan sansani. Babu shakka shugabannin Arewa sun nuna wa duniya cewa Arewa Jiha ce Mai Bambanci Da Ban mamaki ta kuma isa ta yi mulkin kanta.

Bukukuwan mulkin kai na watan Mayun shekarar 1959 zai sanya a yi tutoci masu tsawon yadi dubu ashirin da uku (23,000). Ana shakka ma ko za a sami waxansu tutocin da ba za a yi amfani da su ba.

Masaqar Kaduna (wadda aka buxe a shekarar 1957 – gini mai faxin eka huxu da rabi duka kuwa ginin a rufi xaya ne) ita ke saqa tufan tutocin, sa'an nan Jam'iyyar Jiyya Reshen Kaduna za su rina su zayyana su yadda ya kamata. Ta haka an yi tsimi ke nan idan aka ce za a yi odan tutoci daga qetare.

Alamar Arewa

Mulkin Kai yana buqatar samun wata alama kamar yajajjiyar tuta, baje da sauransu na Majalisar Gudanarwa ta qasa. An yi shawara kan baje, saboda haka

---

[1] *Nig. Citizen*, Asabar, 9/5/1959, shafi na 8

[2] *Ibid.*

daga 15 ga Maris xin shekarar 1959, abin nan da aka saba sani qullin Arewa wato"Northern Knot" (zayyanar da ake adon riguna da ita a gicciye da kafaxa, wanda ada ana kiransa "Kano Knot") za a xauke ta don ta zama alamar Jihar Arewa. Wannan alama za a riqa buga takan takardu, motoci da kayyaki na gwamnati.[1]

Tutar Arewa: Kuma an yi ta da ratsin launin zinare a kan launi mai ruwan ciyawa xauke da qullin Arewa a tsakiya. Wannan tutar 'yan Majalisar Zartarwa za su riqa amfani da ita kafin a samu 'yancin qasa a shekarar 1960.

Hatimin Arewa: Kwalejin London wato *College of Arms*, itace ta zana hatimin Arewa, Majalisar Zartarwa ta amince ta kuma miqawa Mai martaba Sarauniya ta kuma sami yarjewarta. Hatimin ya qunshi wani garkuwa da ke da zanen sa da ganyen dawa a sama, da akuya da ganyen masara a qasar sa. Akwai ratsin layi a tsakiyarsa da ke nuna alamar sadarwa. Akwai doki a gefen hagu da raqumi a gefen wannan garkuwa. A bisansa akwai littafi da takobi bisa (matashin) auduga da gyaxa. Taken Jihar Arewa kuwa shi ne: Aiki da Ibada.[2]

An yarda da iqirarin Arewa bayan ta sami Mulkin Kai ya zama "Aiki da Ibada." Shi ne kuma za a sanya kan *Coat of Arms* wato hatimin Arewa. Saboda qarin yawan 'yan Majalisar Wakilai ta Arewa, to, idan an sami 'yanci a shekarar 1959, ya zama dole a gina sabon xakin Majalisa kusa da *Lugard Hall*. Majalisar Sarakuna za su riqa taro a ciki su kaxai. Dukkan Sarakunan da aka shaida da su, za su zama 'yan Majalisar Sarakuna.

Duke da Duchess of Gloucester za su walkilci Sarauniya da Duke of Edinburgh lokacin bukukuwan Mulkin Kai a watan Mayun shekarar 1959. Har ma an roqi Duke da ya aza harsashin ginin xakin taron Majalisar Wakilai, a lokacin wannan ziyara tasa. Yanzu dai gine-ginen ofisoshi sun kai lokacin da za a ga zayyana mai qawa da aka yi musu. Yawancin mutane suna yabawa da waxannan gine-gine, don kuwa samfurin zayyanar irin na qasashen Musulmi Baqar Fata ne.

Lambobi: Wani shararren kamfani na *Birmingham* ta Ingila da ke yin lambobi, an ba shi odar ya qera lambobin tunawa da mulkin kan Arewa guda miliyan xaya (1,000,000), a kan lambobin har da suffar *Lugard Hall*. Za a sayad da su araha ga mutane. Za a kuma yi amfani da dubban lambobi ga bayarwa kyauta. Akwatuna arba'in (40) da ke da lambobi dubu maitan da hamsin (250,000) cikinsu har sun iso qasar nan ko.

Wasan Tatu: Qila kamar sojoji dubbai da ke zaune a Kaduna za su shiga cikin wani wasan Tatu da za a haskaka lokacin bukukuwan mulkin kan Arewa. Qila ana zaton shi ne zai zama wasan Soja mafi kyau da aka tava nuna wa jama'a a duniya.

---

1 GTK 19/12/1958, shafi na 7

2 NC, Asabar, 14/3/1959, shafi na 19

Ko da yake samun 'yanci ya gamsar da balagaggun 'yan Nijeriya ta Arewa, haka kuma zai za ma wani alfanu ga samarin qasar nan. Su ma za su yi irin nasu wasannin. Kwamitin kula da 'yan makaranta zai shirya wasa da 'yan makaranta za su yi a ranar Sati 16 ga Mayu. A wannan rana ce za su yi wasanni da za su nuna bunqasar ilimi a Arewa, su kuma taru su yi qawanya a filin wasan da zai nuna taswirar Jihar Arewa. Waxannan 'yan makarantar sun haxa da 'yan *Scouts*, da *Girl Guides* da kuma *Boys' Brigades* da Sauransu.

Aqalla yara dubu haxu (4,000) ne za su yi waxannan wasanni masu qayatarwa. Dubu ashirin (20,000) daga cikin su sun fito ne daga lardunan Arewa. Kowace lardi an buqaci ta aiko da aqalla 'yan Makaranta xari (100). An kuma kwaso qarin xari takwas daga lardunan da ke da makarantu mafi yawa. 'yan kwamiti sun tanadi isashen mahalli ga waxannan xaruruwan 'yan makaranta Samari da 'yan Mata waxanda suka zo musamman don su qasaita shagulgulan samun 'yancin Jiharsu.[1]

Xaya daga cikin shirye-shiryen bukukuwan mulkin kai a watan Mayu na shekarar 1959, shi ne hanyar da 'yan Nijeriya da "Turawa" su ke aiki tare, sa'an nan sau tari suke haxa qarfinsu don su sanya bukukuwan su zama abin da ba za a manta da shi ba har abada, tilas ne a ba da taimako na kai. Misali, filin wasan golf, za a karve shi don nuna fasahan aikace-aikacen gwamnati, sana'oi da ciniki na Jiha. Akwai runfunan da aka ware na ofishin Ministoci da ma'aikatun da suka yi wajen in ganta wannan Jiha.

Za a yi wasan kwaikwayo na nuna majalisar qauye mai kyau da mara kyau. Za a nuna taswurori da hotuna da aka xauka cikin jirgin sama. Akwai kuma injin xaba'i wanda tare da Ma'aikatar Ba da Labarai ta jiha za su riqa ba da labarai kullum. Rumfa ta biyu na kamfunan da ke yin wani abu a Jihar nan ne, za a kira "Rumfar Abubuwan da Aka yi a Nijeriya ta Arewa." Manyan kamfuna da qanana za su shiga. Rumfa ta uku za ta xauki kantunan da suka daxe suna mu'amalarsu a Arewacin Nijeriya – tare da sabbin kantuna. Zai ba da dama ga jama'a su ga irin taimakon da waxannan kantuna ke yi.

Bayan bukukuwan Mulkin Kai, duk qarfunan da aka yi amfani da su wajen gine-gine za su za ma masu amfani ne. Waxansu qarfunan za a yi amfani da su wajen ginin runfunan kasuwanni, sa'an nan manyan qarfunan za a gina makarantu da su. An ce lafiya uwar jiki babu mai fushi da ke. A duk inda jama'a da yawa za su yi taro, tilas a tabbatar da tsaro da kare lafiyarsu. An xauki duk waxannan matakai a lokacin shagulgulan murnar samun Mulkin Kai.

---

[1] NC, Asabar, 14/3/1959, shafi na 19

Kare Lafiyar Jama'a

Dubban mutane za su kwararo zuwa garin Kaduna saboda bukukuwan samun mulkin kai da za a yi a watan Mayu na shekarar 1959. Ma'aikatar Lafiya ta xauki qwararan matakai don ganin an kare lafiyar waxannan mutane, an kuma hana varkewar ciyuka. A dalilin haka ne aka yiwa baqi da 'yan gari da ke Kaduna allurar rigafin ciwon agana wato *Smallpox*. Ma'aikatan lafiya sun yiwa dubban mutane wannan allurar rigafi a Sabon Gari, da Tudun-Wada, da ofisoshin gwamnati da shagunan 'yan kasuwa, har da mazauna shiyyar gwamnati wato *Government Reservation Area*. Tun daga farkon watan Fabrairu aka fara wannan muhimmin aiki, kafin 25 ga Maris har an yiwa mutane dubu talatin (30,000) wannan allurar.

Don a sauqaqa wannan aiki duk wanda ya shigo yankin Kaduna da ke da nisan kilomita ashirin daga Gidan Waya ta kowace fuska ya zama tilas ayi masa lambar rigafin ciwon agana. Saboda haka duk wanda ya zo Kaduna ta Jirgin Sama, ko Jirgin qasa ko ta mota ko bisa dabba ko a qasa, to, wajibine ya samu wannan rigafi. An kuma tanadi wuraren da ake yi wannan rigafi a ciki da wajen Kaduna waxanda suka haxa da: (i) A Rigacikun a kan hanya Jos zuwa Zariya, (ii) A hanyar Kachiya, kusa da qaramin Gidan Yari, (iii) A titin Mando, kusa da filin jirgin sama, (iv) A Eaglesome road, inda akwai jama'a da yawa, (v) da Kaduna Jamsin, (vi) Tashar jirgi ta Arewacin gari da sauran wurare da suka dace.

A duk waxannan wurare ake binciken fasinsojin motocin haya, don a tabbatar da kowa ya yi rigakafin wannan mummunan ciwo. Haka kuma ma'aikatan lafiyana la'akari da sauran cutuka kamar ciwon amai da gudawa, da atini, da ciwon tari da ciwon sanqarau, da sauransu. Ma'aikatar Lafiya ta xauki matakan hana varkewar annobar waxannan cutuka.[1]

Tsabtar Gari da Muhalli

Tun daga watan Fabrairu na shekarar 1959, aka xauki matakan tsabtace garin Kaduna Yankin Hedkwata, xaya daga cikin shirye-shiryen bukukuwan murnar samun mulkin da Arewa za ta yi a watan Maris mai zuwa. Ministan Lafiya na Jihar Arewa, Alhaji Ahman Galadiman Pategi, da manyan jami'an babban jami'in kula da lafiyar da suka haxa da Dr. E. Simpson da Malam A. K. Muhammad, babban Baturen 'yan Sanda mai riqo, suka zagaya wasu layukan wannan gari domin su duba yadda tsabtar garin take, suna bi layi da qwararo da wajajen zubar da shara.

---

[1] NC, No. 714, Wed. 25/3/1959.

A wannan ziyara sun duba layin Prince Edward, da Jos Road, da Zariya Road, da Abeokuta Street, da Sokoto Road, da Lagos Street, da Market Road, dukkan su a sabon garin Doka. Ministan Lafiya ya yi amfani da wannan dama, ya kira jama'a da kada su riqa zubar da shara a wuraren da ba su kamata ba saboda su kan toshe magudanar ruwan kwalbati wanda ke qara qazantar waje, ya sanya waje ya riqa wari tare da qarin qwari da qudaje.

Shi kuma Malam A. K. Muhammad, sai ya shaida wa jama'a cewa haqqinsu ne su kula da muhallinsu da kuma gujewa watsa shara a ko'ina. A wannan lokaci har an hukunta wajen mutane goma waxanda aka samu suna watsa shara ba a wajen da ya kama ta ba. Ya kuma ce hukumarsa na da qarancin ma'aikata saboda haka Kaduna ke da Jami'an Duba-Gari guda uku kacal!

A lokacin da Ministan Lafiya ke duba Lagos Street, sai ya ga wani waje da aka zubar da bayan gida. Saboda haka sai ya ce da babban Jami'in kula da lafiya, "rashin tsabtace layuka da lambatu, matsaloli ne da ke haifar da yawan mutuwar jarirai." Dr. Simpson sai ya qara da cewa, ana jin a cikin jarirai dubu (1000) da aka haifa a Nijeriya, xari biyar (500) ba sa kaiwa ga shekaru biyar!

Ita wannan ziyarar ba zata da Ministan Lafiya ya kai don wayar da kan jama'a domin su tsabtace mahalli da kuma tashi tsaye wajen shirye-shiryen karvar baqin da za su zo garin Kaduna a watanni masu zuwa.[1]

Nunin Kaduna

Kwamitin Nunin Kaduna ne ke da alhakkin haxa qasaitaccen Nunin Kaduna wato Kaduna *Exhibition* a lokacin shagulgulan samun mulkin kai. Shi wannan Nuni za a yi shi ne don nuna ci gaban Jihar Arewa ta fannonin ilimi da fasaha, da kasuwanci. A wannan lokaci za a baje kolin kayayyakin da Arewa ke yi a masaqunta na gargajiya, da hikimar maqera da marina da sauransu. Wannan baje koli, zai ba da dama ga kamfanonin qetare da su bada gudunmawarsu wajen havaka Jihar Arewa.

Irin wannan baje-koli da aka yi ya dace da kowane zamani, ya kuma xaga martabar Arewa ainun. An zuba leburori wajen xari biyar da jami'an aiki da suka qunshi masana fannonin nuni iri-iri da suka yi wajen xari biyu da saba'in. Duk sun duqufa suna aiki tuquru wajen qawata sashe-sashe a wannan baje-koli. A kwai runfuna fiye da sittin da kamfanoni arba'in da biyar duk sun baje kolinsu. Ma'aikatar Waya ta P and T ta sanya wajajen telefon arba'in da bakwai a sassa daban-daban na wannan fili. Akwai kuma kafafen sadarwa, a ko'ina inda ake ba da sanarwa ko cigiya, idan mutum ya vata ko kuma ana buqatar ba da da wata sanarwa ga ximbin jama'a da suka hallara a filin Nunin Kaduna. Kamfanin G.O.

[1] NC, 14/2/1959

Olivant ya taimaka da kafa wajajen wayar telefon mai rahusa ga jama'a a wannan ranar biki.[1]

Shugaban Baje-Koli M.J.A Clewley, ya bayyana cewa gwamnatin Jihar Arewa ta kashe fam dubu arba'in da shida (£46,000) wajen wannan Nuni. Sa'annan kamfanonin 'yan kasuwa sun ba da gudunmawar fam dudu sittin da biyar (£65,000).

A wannan biki 'yan Scout da Girl Guides sun yi kaxe-kaxe da raye-raye da suka qara wa bikin armashi. A wannan lokaci ne ma aka gabatar da ma'aikatan da suka shirya wannan Baje-Koli ga Firimiyan Arewa, wanda ya riqa yi masu tambayoyi akan kayayyaki daban-daban da aka baje-kolisu. Duk ma'aikatan sun nuna qwazo da sanin aiki, sun kuma taimaka wa jama'a da suka zo don su ga ayyukan ci gaban da Jihar Arewa ta samu na shekaru hamsin. Babu shakka kwalliya ta biya kuxin sabulu.[2]

Ko ta wace fuska wannan Nuni ko Baje-koli ya qayatar sosai. Don kuwa a wannan lokaci an nuna ci gaban da mutanen Arewa suka yi a cikin shekaru hamsin. A wancan shekaru da suka shuxe Arewa ba ta da kayayyakin da take kaiwa qetare masu daraja sosai, amma sai ga yanzu bayan shekaru hamsin tana aikawa da kayan gona qetare da suka kai na fam miliyan arba'in da bakwai (£47,000,000) a shekara.[3] A wannan lokaci arziqin qasar a Arewa take don babu Jiha mai wannan arziqi. Wannan Baje-kole babu shakka ya sa an qara tsinkewa da Arewa.

Kyautar Sha-tale-tale

A safiyar Alhamis 14 ga Mayu 1959, Mai girma Firimiyan Jihar Arewa, Sir Ahmadu Bello, ya karvi kyautar Sha-tale-tale da wani kamfanin haqar Kuza mai suna Chamber of Mines, ya gina akan titin Kaduna zuwa Zariya, ya kuma baiwa Arewa kyauta. Shi wannan Sha-tale-tale an qawata shi sosai, yana watsa ruwa sama an kuma kewaye shi da fulawoyi masu kyau. An gina shi Arewa da Gidan Shawara akan mahaxar titin Kaduna zuwa Zariya da na *North Road* da ke daura da Gidan Shawara.

A lokacin da yake qarvar wannan kyauta, Firimiya a jawabinsa, ya bayyana godiyarsa ga wannan kamfani ya kuma yabawa waxannan mahaqa kuza da suka taimaka wajen bunqasa Arewa, musamman Lardin Filato da abubuwan ci gaba. Ya ce ba za a manta da gudunmawayar da mista Foley, da Lawes, da Cooke da Butter, suke yi ba waxanda su ne kan gaba wajen ciyar da Arewa gaba, har ta kai

---

1 *Nigeria Citizen*, Asabar, May 9, (1959), shafi na 8

2 *Nigeria Citizen*, Asabar, May 9, (1959), shafi na 8

3 *Ibid*., May 15, 1959, shafi na 3

matsayin da take a yanzu. Har ila yau, ya yaba masu wajen horar da 'yan Nijeriya musamman 'yan Arewa.[1]

Duk shirye-shiryen da aka yi a watan Mayu na shekarar 1959, an yi su ne domin Arewa ta nuna murnar samun Mulkin Kai da kuma qasaita. An kuma yi kyakkyawan shirin karvar ziyarar Duke da Duchess daga gidan Sarautar Ingila.

Ziyarar Duke da Duchess

Kaduna Yankin Hedkwata ya karvi baqunci manyan baqi masu Martaba Duke da Uwargidansa Duchess of Gloucester, waxanda suka zo takanas don su taya 'yan Arewa murnar samun 'yancin Jiharsu. Kaduna ta saba da samun irin wannan ziyara. Sarauniyar Ingila Elizabeth ta Biyu ta kawo ziyara a shekarar 1956, sa'an nan Gimbiya Royal ta zo a shekarar 1957. Bayan shekara biyu sai ga manyan baqi Duke da Duchess na Gloucester sun biyo sawu a shekarar 1959. A duk ziyarce ziyarcen manyan baqi da garin Kaduna ke samu babu kamar wannan ziyarar taya Arewa murnar samun Mulkin Kai wajen yawan qasaitattun mutane kuma abokan Arewa masu yi mata fatan alheri da ci gaban jama'arta daga qasar Ingila.

Saboda haka sai aka yi muhimmin shirin karvar waxannan baqi. Ministan lafiya Alhaji Ahman, Galadiman Pategi bai samu sukuni ba saboda qoqarin ganin an tsabta ce garin Kaduna sosai, jama'a kuma sun cikin qoshin lafiya da kyawawan mahallai. A sabili da haka Ministan da jami'an tsabta suka zagaya garin domin gani ya kori ji. Ma'aikatarsa ta yi aiki tuquru wajen ganin garin Kaduna na shirin karvar baqin.

Masu Martaba Duke da Duchess za su kawo ziyarar kwana goma an kuma yi shirye-shiryen abubuwan da za su yi a wannan lokaci kamar haka: Za su iso Arewa ran 13 ga Mayun shekarar 1959. Masu Martaba za su sun iso filin jirgin saman Kano ran Laraba da misalin qarfe 7:30 na safe. Gwamna-Janar Sir James Robertson, da gwamnan Kaduna Sir Gawain Bell da Firimiya ne suka tarye su su ka yi masu lale da marhabin. A safiyar wannan rana ce suka kai ziyara ga fadar Sarkin Kano Alhaji Sir Muhammadu Sunusi aka kuma zagaya da su wasu wurare a birnin Kano. A wannan lokaci ne ita Mai martaba Duchess ta shiga gidan Sarki inda ta gana da iyalansa kamar yadda Sarauniya ta yi.

Da La'asar sakaliya, da misalin qarfe 4:15 na Yamma manyan baqin suka baro Kano ta jirgin sama zuwa Kaduna. gwamnan Kaduna da Firimiya ne suka tarye su da saukarsu a wannan filin jirgin sama. Wato a wannan rana ce Duke da Duchess suka iso garin Kaduna Hedkwatar Arewa.

Ita wannan ziyara tana da muhimmancin gaske a tarihin Jihar Arewa. Arewa kuma a shirye take a kowane lokaci da ta nuna so da qauna da biyayya ga qasar Ingila. Kaduna ta ga manyan baqi da suka zo daga Ingila da sauran qasashen

[1] *Ibid.*

duniya, waxanda suka zo don su tayata murnar samun Mulkin Kai. Mr. Allan Lennox-Boyd Sakataren Mulki, wanda a lokacinsa wannan Jiha ta samu yanci, yana xaya daga cikin manyan baqin da suka baqun ci Kaduna a wannan lokaci.

Tsofaffin gwamnonin Arewa waxanda suka haxa da Sir Eric Thompstone, da Sir Bryan E. Sharwood-Smith da kuma Gwamna mai barin gado Sir Gawain Bell duk sun hallara cikin farin ciki tare da annashuwa don taya Jihar da suka rena har gashi ta girma, har ma sun zo bikin yaye ta. Haka kuma sauran Firimiyoyin Jihohin Nijeriya har da Mr Foncha na Kudancin Kamaru sun zo don nuna goyon bayansu da qara danqon zumunci.

A wannan lokaci na bukukuwa iri-iri ne Firayim Ministan Nijeriya da Firimiyan Arewa suka ga kwararowar manyan mutane ta ko'ina daga sassan duniya, waxanda suka taho takanas don su nuna farin cikinsu tare da fatan alheri. Arewa kuma ai Jiha ce mai bambanci mai kuma ba da mamaki. Saboda haka dubban baqin da suka zo sai da suka tsinke da al'amarin Arewa, dubban kuma sun sallama mata. Amma ai banza bata kai zomo kasuwa. Qasaitaccen shirin da aka yi wa garin Kaduna ya yi tasiri qwarai da gaske. Saboda Arewa ta basu mamaki qwarai da gaske.

Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, ya qware wajen tsara shirye-shiryen bukukuwa irin waxannan tun daga ziyarar Sarauniya, shekaru uku da suka wuce, wato tun a watan Fabrairun shekarar 1956. Saboda shi ya jagoranci Majalisar Kwamitin shirye-shiryen bukukuwan da za a yi a Kaduna a cikin watan Mayun shekarar 1959 saboda murnar samun mulkin kan Jihar Arewa. Ita wannan majalisa tana da qananan kwamitoci guda goma sha-bakwai a qarqashinta.

Kowane kwamiti nada aiki na musamman da aka xora masa wanda zai aiwatar cikin tsari da gaggawa. Haka kuma kwamitocin dukkansu suna aiki ne baki xaya ba tare ba vata lokaci da. Akwai kwamitin kula da Baqi daga qetare, da kwamitin Daba, kwamitin karvar baki daga qetare shike da alhakkin gayyatar manyan baqi daga qasashen waje. Waxanda za su wakilci Sarauniya Ingila su ne Masu Martaba Duke da Duchess na Gloucester da Sakataren Mulki Mr. Alan Lennox-Boyd. Saboda ayyukan Daba suna da yawa sai aka raba kwamitin Daba gida huxu kowane na cin gashin kansa, kamar haka:

Kwamitin Daba: Shi wannan kwamiti nada alhakkin shirya da ba irin na zuwan Sarauniya a shekarar 1956, amma ya fi wannan dabar qasaita da ban mamaki. A dalilin haka sai aka raba kwamitin zuwa qananan rassa guda huxu, kowane da aikinsa daban-daban.

Wannan kwamiti ne aka xorawa alhakkin yin qasaitacciyar Dabar da zata share wa kowace daba da aka tava yi zane. Itace zata samar da lafiyayyun dawakai guda dubu uku (3,000) ta kuma tara mutane dubu takwas da xari biyar (8,500) waxanda dukkansu su hallara a filin sukuwa (Murtala Square) a ranar 15

ga Mayun shekarar 1959.[1] Kwamitin tsara wajen da jama'a da manyan baqi za su tsaya ko su zauna, su kuma aikinsu dabam. Aikin wannan kwamiti shi ne ya tsara wajen zaman manyan baqi wanda zai xauki aqalla mutane dubu uku da dari huxu (3,400). Shi wannan dandamalin manyan mutane za a qawata shi da irin zane-zane gidajen Sarakunan Arewa, a kuma yi masa wajen zaman baqi na musamman mai qawatarwa wato Pavilion inda Duke da Duchess da Gwamna da Firimiya da sauran manyan baqi za su zauna. An kuma gina wannan dandamali bisa tudu ta yadda mazauna za su ga fili sosai ba tare da an yi masu shamaki da komai ba.

A wajen tsayawan sauran jama'a kuma, shi ma an yi masa gyaran da ya dace sosai. An zagaye filin sukuwa gaba xaya. A kuma wasu sassa a harabar filin an yi wajen kula da marasa lafiya da gaggawa, da wajen yin wayan tarho, da tsangayar masu xaukar labarai da runfar masu aikin rediyo, sa'anan akwai masai masu yawa da aka gina a wurare, a duk kusurwowin wannan fili don masu buqata. Haka kuma akwai famfuna da ke ba da ruwan sha ga xaruruwan jama'a masu yawa.[2]

Irin wannan qasaitaccen shiri ba wanda zai iya haxa shi kamar Sir Ahmadu Bello. Saboda haka ne ake yawan ganinsa ya kai mari ya kai gauro, yana duba duk ayyukan kwamitocin don kada a samu miskila wajen yin abu da zai zama gagara – koyo. Shi ma kansa madugu uban tafiya, Firayim Ministan Nijeriya, Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa bai samu ta zama ba. Don haka ya taso takanas daga Ikko don ya ganewa idonsa irin qasaitaccen shiri da aka yi. Da zuwansa wannan fili sai amininsa Firimiya ya zagaya da shi lungu-lungu na wannan filin Daba.

A filin sukuwa inda aka yi qasaitacciyar daba, akwai xaruruwan xakunan kwano da runfunan zana masu yawa. Kwamanda wannan fili shi ne Mr. R.N. Jacobsen wanda ya bayyana cewa filin daba yana da faxin eka xari uku da sittin (360) da kuma tituna masu nisan mil huxu da aka dave da kwalta. Sa'anan filin na xauke da mutane 10,700 da dawakai 3,000. An shirya abubuwan da masu Martaba za su yi bi-da-bi, a lokacin wannan muhimmiyar ta su.

A ranar Alhamis 14 ga Mayu, da misalin qarfe 11:00 na safe masu Martaba suka gana da 'yan jaridu a Gidan Gwamnati. Da qarfe biyar na Yamma suka zagaya sansanin daba wato Dabar Camp inda Mai girma Duke ya duba sansanin 'yan Scout. Da qarfe 8:15 na dare suka halarci wata liyafa da aka shirya masu a Gidan Gwamnati.

Ran Jumu'a 15 ga Mayu, itace babbar ranar da aka yi masu qasaitacciyar Daba. A safiyar wannan rana ce da qarfe 8:30 suka baro Gidan Gwamnati zuwa Sansanin Dabar, inda suka zagaya sansanin a buxaxxiyar Motar *Landrover*. Manyan baqi sun hallara a *Lugard Hall* da qarfe biyar na Yamma. Da qarfe 9:15

---

[1] NC, Asabar, 14/3/1959, shafi na 18

[2] NC, Asabar, 14/3/1959, shafi na 18

suka yi kallon kaxe-kaxe da raye-rayen wasannin gargajiya a farfajiyar gidan gwamnati.

A ranar Sati, 16 ga Mayu da misalin qarfe 8:30 na safe ne Duke da Duchess suka koma filin sukuwa inda suka ga wasanni da faretin 'yan Makaranta. Bayan wannan ne sai suka ci abincin rana da manyan sojoji a Army Mess. Manyan baqi sun huta a ranar Lahadi 17 ga Mayu. A ran Litinin 18 ga Mayu Duke da Duchess sun tafi *Lugard Hall* wajen bikin aza harsashin gina Zauren Taro na 'yan Majalisa, da misalin karfe 8:30 na safe. Sun kuma halarci Nunin Kaduna da qarfe 9:15 na safe.

A wannan rana ce kuma Duchess ta buxe Makarantar Koyon Aikin Nas da misalin qarfe 5:00 na Yamma. An kuma yi qasaitacciyar liyafa a Gidan Gwamnati da karfe 7:45 na dare.

Ran Talata 19 ga Mayu, masu Martaba suka kai ziyara birnin Zazzau, inda suka karya kumallo da Razdan na Zariya. A safiyar wannan rana suka ziyarci barikin Sojan *Boy's Company of the Queen's Own Nigeria Regiment*, da Makarantar Koyon Aikin Mulki da Army Mess. Bayan sun ci abin rana da Razdan, masu Martaba sai suka kai ziyara ga Cibiyar Bincike, "Research Station" da ke Samaru. Da qarfe 6:00 na Yamma suka dawo Kaduna don su halarci wasan soja da ake kira *Military Tattoo*.

A ranar Laraba, 20 ga Mayu za suka bar Kaduna zuwa garin Jos inda za su huta a Tudun-Wada har ya zuwa ranar Jumu'a inda za su ziyarci wajen Haqar Kuza, da wajen aikin lafiya na Mishan da ke Vom da Ma'aikatar Binciken qudan tsando, W.A.I.T.R da Ma'aikatar kula da lafiyan Dabbobi da Gandun Daji. A ranar Sati 23 ga Mayu masu martaba za su bar garin Jos zuwa Enugu. An yi shagulgulan murnar samun Mulkin Kai a sauran manyan garuruwan Arewa kamar Sakkwato, da Zariya da Kano da Maiduguri da sauran su.

Bukin Mulkin Kai a Sakkwato

A ranar lahadi aka yi qasaitaccen bikin samun Mulkin kan Nijeriya ta Arewa a garin Sakkwato. A wannan rana ce mutane fiye da dubu ashirin (20,000) suka hallara daga ko'ina a lardin Sakkwato, inda aka yi wata qaramar Daba. Dawakai kusan dubu uku suka yi hawan nuna qasaita a wannan Daba. Manyan mutanen da suka halarci wannan Daba sun haxa da, Firimiya Alhaji Sir Ahmadu Bello da gwamnan Jihar Arewa Sir Gawain Bell da Uwargidansa Lady Bell da sauran manyan baqi.

A ran sati aka fara bikin a fili mai faxin murabba'in mil guda wanda ake kira Hurumi saboda a wannan waje ne Askarawan Daular Usumaniyya da yawa suka yi shahada shekara 56 da suka wuce, wato a shekarar 1903. A lokacin da aka tafka mummunan yaqi da su da sojan Turawa xauke da manyan bindigogi da igwa. Tun

daga wannan rana ce aka riqa wasan wuta, da raye-raye ga barade cikin kayan yaqi xauke da kibiyoyi da masu da baka da kwari da makamantansu.

Daga misalin qarfe 8:00 na safe karabitin 'yan Sanda suka hallara a filin Daba. Amma ba a fara bikin ba sai da qarfe 2:30 na Yamma saboda jiran su Firimiya da Gwamna da suka iso ta jirgin sama daga Kaduna. Duk Hakiman lardin Sakkwato arba'in da bakwai da manyan ma'aikatan En'e sun hallara a wannan fili ana jiran zuwan manyan baqi. Bikin a Sakkwato yana da muhimmancin gaske. Na farko yana nuna qarshen Mulkin Mallaka a Arewa. Na biyu kuma a garin Sakkwato ne Hedkwatar Daular Usumaniyya, Turawa suka angije wannan Daula a shekarar 1903. To, bayan shekaru hamsin da shida sai wannan jiha ta samu Mulkin Kanta a qarqashin jikan-jikan Shehu Mujaddadi wato Sir Ahmadu Bello.

Saboda haka sai aka yi bikin samun mulkin kai a dai-dai inda Sojan Ingilishi suka kai nasara akan askarawan Daular Usumaniya. Akwai itacen Kuka da itacen Giginya a dai-dai wajen da aka gwabza wannan yaqi a shekarar 1903. Amma itacen giginyar ya mutu sai aka dasa wani don tarihi. A wannan rana ce kuma aka haifi Sarkin Musulmi Sir Abubakar na uku, a ranar wannan biki ne ya cika shekara 56 da haihuwa. Bikin samun mulkin kai sai ya haxe da bikin ranar da aka haifi Sir Abubakar.

A wannan rana bayan Sarkin ya yi jawabinsa da kuma jawabin Firimiya sai Hakimai a cikin kayan yaqi suka zo xaixai da xaixai suna yiwa Amirul-mumina jinjinar gaisuwa ta mubaya'a. Suka kuma kai gaisuwar ban girma ga Gwamna da Firimiya.[1]

Duke da Duchess a Zariya

Dubban jama'a daga kowane lungu na Lardin Zazzau sun halarci bikin samun Mulkin kai da aka yi a filin Babban Dodo a ranar Lahadi a Zariya. A gaban dubban jama'ar wannan lardi ne Sarkin Zazzau Ja'afaru ya yi jawabinsa inda ya ce ya godewa Allah Mai girma da ya ba da ikon samun Mulkin Kai cikin lumana. Mulkin Arewa da Turawa suka karva ta yaqi da zubarda jini, shekaru hamsin da shida da suka wuce. Sarkin ya kuma yi kira ga jama'arsa da cewa don Girman Allah, kowane mabiyin addini ko qabila da su haxa kai da shugabanni domin a samu babban ci gaba. Ya ce in babu haxin kai da aiki tuquru samun Mulkin zai ci tura ba kuma zai amfanarda komai ba. Ya kuma yi kira da jama'arsa da su haxa kai kada su rarrabu. Sarkin Zazzau ya umarci jama'a da su zama masu girmama addini da al'adun kowa saboda samun zaman lafiya da kwanciyar arziqi. Ya kuma yi addu'a ga Ubangiji da Ya Albarkaci kowa.

Kafin Sarki ya yi jawabinsa, kuwa sai da Razdan Mai riqo, Mr. A.C.E Long tare da manyan ofisoshinsa biyu dukkansu cikin kayan aiki akan dawakai ya zaga

[1] NC, Wed., 18/3/1959

faretin Sojan *QONR Depot*, da *Boys Company*, da *Nigeria Police* da *N.A Police*, da *Boy Scouts*, da *Girl Guides* da *Red Cross* da 'yan Makaranta daga makarantun da ke Zariya. Bayan haka sai ya hau dandamalin karvar gaisuwa inda ya tsaya, yana karvar gaisuwa daga faretin 'yan Sanda da sojoji da 'yan Makaranta. Daga nan sai ya karanta jawabin gwamnan Arewa Sir Gawain Bell ya kuma isadda fatan alherin Firimiya.[1]

Masu Martaba Duke da Duchess sun kai ziyara birnin Zazzau. Ita Duchess ta kai ziyara fadar Sarkin Zazzau shi kuma Duke ya tafi Makarantar Koyon Aikin Gona da Bincike da ke Samaru. A lokacin da Duchess ta tafi fadar Mai girma Sarkin Zazzau an yi mata lale da marhabin. Wasu ayarin 'yan Mata da ke Makarantar Islamiyya a Fadar Sarki ne suka taryeta ita da 'yar rakiyarta Lady Bell. A cikin 'yan wannan makaranta har da qananan 'ya'yan Sarki, Muhammadu Bashiru da Aminu, duk kansu kuma sun ci ado mai qawatarwa. Su kuma 'yan makarantar na sanye da rigunan khaki da xankwali mai launin ja, sun kuma qawata qofar fada sosai a lokacin bikin karvar wannan babbar baquwa da ayarinta.

Ita ma Duchess ta ci kwalliya, tana sanye da xantofi wato siket mai launin ruwan qwai da farar malfa. Itaka kuma Lady Bell ta ci ado ne a shuxin siket. Da isowarsu qofar shiga faxa sai Mai girma Sarkin Zazzau ya gabatar da su ga 'yarsa gimbiya Maryam 'yar shekara bakwai wadda ta ci ado da farar riga. Bayan ta gaida manyan baqi sai ta miqa wa Duchess kyautar qunshin filawoyi.[2] Komai ya ba da sha'awa, baqi kuma na cike da farin ciki.

Bayan ta gaisa da manyan mutane a fada sai Martaba ta shiga cikin gidan Sarki wajen iyalansa, ta sami misalin minti goma sha-biyar (15) tana ganawa da matan Sarki. Daga nan sai ta fito da ayarinta, ta yi bankwana da Sarki da jama'arta ta komo Kaduna a cikin mota.

Shi kuwa Mai girma Duke ya isa Mai Makarantar Koyon Aikin Gona ta Samaru ne da Qarfe 4:45 na Yamma, tare da ayarin 'yan rakiya waxanda suka haxa da gwamnan Arewa Sir Gawain Bell da Firimiyan Jihar Arewa Sir Ahmadu Bello. Ministan Gona, Malam Mustafa Monguno ne ya karve su ya kuma gabatar da sakataren Binciken Aikin Gona, Mr. J.H. Gisborne da Sakataren horarwa, Mr. D.T.R Elsmore da babban jami'in Gona Mr. Jefferson.

A wannan lokaci sai Mr. Gisborne ya gabatar da Shugaban Makarantar, Mr. D. Westwood da manyan ma'aikata da xalibai. Yana gama zaga ya wurare a wannan makarantar sai ya sanya hannu a Littafin Baqi masu ziyara na wannan Makaranta kafin ya wuce zuwa Cibiyar Bincike wato *Research Station*.

---

[1] NC, Asabar, 23/5/1959

[2] *Ibid*.

Da isar Mai martaba *Research Station*, sai Sakataren Cibiyar ya yi taqaitaccen bayani a kan ayyukan bincike daban-daban da Cibiyar ke yi da kuma nasarorin da ta samu. A wannan lokaci ne ma har aka nuna wa Mai martaba kayayyakin shuka, da shanun noma da taraktan aikin gona. Shi kansa ya nuna sha'awarsa ga garman noma da kuma kixan noma da ake yi a lokacin huxa. Har ila yau an nuna wa manyan baqin injunan casar gyaxa da sauran kayayyakin aikin gona waxanda ake amfani da su a Arewa.

Daga nan sai manyan baqin suka tafi wajen inganta qasar noma wato *Soil Conservation* da ke da nisan mil biyu da wannan Cibiyar Bincike. Bayan sun dawo da miniti goma sha-biyar sai suka tafi Makarantar Koyar da noma ta biyu, a inda suka ga yadda ake kayayyakin noma da shanu da kuma yadda ake amfani da su. A wannan lokaci ne aka nuna wa Mai martaba wani waje da ke nuna yadda zaman qauye yake a Arewa. Ko bai sami damar ziyarar wani qauye a Arewa ba, wannan misali zai gamsar da shi sosai. Da misalin qarfe 5:45 na Yamma Mai martaba Duke da Gwamna da Firimiya suka bar Samaru. Manyan baqin da ayarinsu sun koma Kaduna ta jirgin sama. [1]

Duchess ta Buxe Makarantar Koyon Aikin Nas

Dubban mutane suka halarci bikin buxe Makarantar Koyon Aikin Nas a Kaduna wadda Babbar Baquwa kuma Duchess of Gloucester ta yi. Bikin ya qayatar sosai. Babbar baquwar ta iso wajen wannan biki tare da matar gwamnan Arewa, Lady Bell da ayarinta. Ministan Lafiya Alhaji Ahman, Galadiman Pategi ne ya tarbi manyan baqi a lokacin da suka iso wannan Makaranta. Da shigowar Duchess harabar Makarantar sai wata xalibar Nas ta miqa mata qunshin filawoyi wata alama da ke nuna maraba da zuwa tare da fatan alheri.

Ministan Lafiya sai ya zagaya da babbar baquwa da ayarinta wannan makaranta, ya gabatar da kwamanda 'yan Qungiyar Agaji, wato *Red Cross* da jama'arsa. An kuma kai ta ga 'yan St. John Ambulance inda aka gabatar da kwamandansu. Daga nan sai wata xaliba ta miqawa Mai martaba Duchess wani makullin azurfa wanda da shi ne ta buxe qofar shiga makarantar. Sa'an nan sai Shugaban Makarantar ta zaga da manyan baqin wurare daban babam na wannan makaranta. Daga qarshe sai Mai girma Duchess ta sa hannu a littafin ziyara na wannan Makaranta. Bayan haka sai ta yi taqaitaccen jawabinta.

A jawabinta, Mai martaba ta nuna godiyarta ga Ministan Lafiya saboda gaiyatar da ya yi mata don ta buxe wannan makaranta, da mahallin xalibai. Ta ce ta yi matuqar farin ciki da yin haka. Saboda ita kowane lokaci mai sha'awar taimaka wa ayyukan Nas ne a Ingila da sauran qasashen waje. Ta kuma bayyana cewa:

---

[1] NC, Asabar, 23/5/1959

Wannan sabuwar makaranta ba kawai wajen karatu ba ne har ma alama ce qwaqqwara da ke nuna niyya da burin shugabannin wannan Jiha wajen baiwa mata dama da qwarzantar su don su ba da gudunmawarsu wajen ciyar da qasarsu gaba.

Ina kuwa fata 'yan mata da yawa za su fito su amfana da wannan babbar damar aka basu. Ilimin da za su samu zai taimake su ko wajen aikin kula da majinyata ko idan sun yi aure. Ilimin zai taimakesu da jama'arsu.

A wannan makaranta za su koyi aikin hannu, za a kuma koya masu tausayi, da sauqin kai da taimako, da natsuwa, halayen da ake buqata ga Nas tagari. Irin Nas da ma'aikatan jinya da ake buqata ke nan waxanda za su zama masu amfani ga al'ummarsu su kuma zama masu farin ciki da alfahari a cikin jama'a.

Ina taya Ministan Lafiya murnar samun bunqasa kula da lafiya ta qarin wannan makaranta, ina kuma miqa farin cikina da fatan alheri ga dukkan malamai da xaliban wannan makaranta, har ma da majiyatan da za su kula da su a nan gaba.[1]

A jawabinsa Alhaji Ahman, Ministan Lafiya na Jihar Arewa ya ce:

A fiye da shekara xari da suka wuce ne, ka tafka wani qazamin yaqi a Turai a kuma gavar tekun "Black Sea", wanda ake kira a tarihi da "Crimean War." A dalilin matsaloli da masifofin da wannan yaqi ya haifar ne, aka samu wata qungiya mai tausayi da son taimakon waxanda yaqi ya kassara. Ita wannan qungiya sai ta zama mai kula da miliyoyin marasa lafiya a duniya baqi xaya.

Wadda ta kafa wannan qungiya kuwa, ita ce Florence Nightingale. A nan sai mu yi tunani muga cewa wannan biki da muke yi a yanzu, ya yiwu ne saboda gudunmayar wannan mashahuriyar mace da ayarinta waxanda suka sadaukar da kansu wajen kula da waxanda suka jikkata a wannan mummunan yaqi.

Kamar sauran qasashen duniya, Nijeriya ta Arewa za ta kafa ingantattun ma'aikatan Nas da za su yi aiki a duk asibitoci da gidajen shan magani a faxin Arewa waxanda ilimi, da gogewarsu da sanin aiki za su yi dai dai da na kowace qasa a duniya.

A matsayina na Ministan Lafiya a wannan gwamnati, ina sane da buqatar da ke akwai ga bunqasar da aikin jiyya a wannan jiha.

---

[1] NC, Asabar, 23/5/1959 shafi na 2

Akwai qarancin ma'aikatan jiyya a asibitocinmu musamman Nas mata da Unguwar zoma. Ana qishirwar waxannan ma'aikata a asibitoci da xakunan haihuwa. Haka zalika qaruwar sabbin asibitoci ya ta'allaqa ne ga samuwar qwararrun Nas da masu kula da majinyata.

Har ya zuwa wannan lokaci an fi samun maza a aikin jiyya saboda haka gina wannan makaranta an yi ne don a samar da isassun Nas mata da kuma ba su damar aikin jiyya wanda ya dace da su sosai saboda halinsu na tausayi da kulawa da taimako. Duk waxannan halaye kuwa an san mata da su.

A yanzu da ake qara samar da abubuwan bunqasa ilimi a wannan jiha na tabbata Yammata da suka dace za su fito su amfana da wannan dama da ke gabansa a wannan Makaranta. Akwai mahalli issashe na xalibai tamanin wanda ya dace sosai ya kuma ba da abubuwan da ake buqata wajen hutu da karatu.

Alamar nasara ce babba ganin an buxe wannan makaranta ne a lokacin da Jihar ta samu mulkin kai. Abun alfahari ne kuma gare ta cewa ta taso tare da Jihar Arewa. Sa'anan kuma ta samu tubarrakin Mai martaba wadda ta buxe ta.

Abu ne kuma mai farantawa yadda makarantar ta taso cikin sa'a da nasara wanda babu shakkar xaliban wannan makaranta za su bi sawun Florence Nightingale wajen aikin kula da majiyyata.[1]

A ziyarar da waxannan manyan baqi suka kawo Arewa a lokacin bukin Samun Mulkin Kanta, sun ziyarci wurare masu daraja da ban sha'awa da dama. Haka kuma sun ga kara da halayen kirki da karimci da mutuncin 'Yan Arewa waxanda ba su da na biyu a wajen biyayya da Sarauniya. A dalilin haka ne Duke ya sami damar nuna godiyarsa da ta jama'rsa ga mutanen Arewa da Shugabanninsu.

Duke ya Gode wa Arewa

Bayan Mai martaba Duke of Gloucester ya isar da saqon Sarauniya ga jama'ar Arewa, sai shi kuma ya gabatar da tasa godiyar ga jama'ar wannan Jihar mai ban mamaki da ban al'ajabi. A jawabin godiyarsa ya ce:

Uwargida na Duchess ta yi farin ciki qwarai da gaske da, rakiyar da ta yi mani zuwa wannan faxexiyar Qasa da kuma saduwa da muka yi da mutane masu karimci da kuma karvar mu da ake yi hannu bibbiyu a duk inda muka ziyarta a wannan qasa.

---

[1] NC, Tuesday 23/5/1959, shafi na 2

Ni kai na, na yi matuqar sa'a da nayi aiki a wata qasa da ke cikin qasashe dake abuta da Ingila, na kuma ziyarci qasashe masu yawa da ke cikin "Commonwealth". Goguwa ta nuna mani cewa babu wata qasa da za ta dogara kacokan a kan albarkatun qasarta kawai amma sai ta yi amfani da naurorin zamani don cin moriyar waxannan albarkatu wajen ciyar da jama'arta gaba kamar yadda naga kuke qoqarin yi a yanzu. Kowace qasa mai tasowa sai ta fuskanci matsaloli waxanda sabon tsarin mulki baya maganinsu sai himma da qwazon jama'ar ne ke kawo sauyi tare da ci gaba.

Na gani sarai qomajin ci gaban da kuke yi zai kai ga nasara. A cikin wannan lokaci kyawawan halayen jama'ar ku da juriya da imanin cewa mutane dai-dai suke a wajen Ubangiji za su taimaka gaya wajen cimma nasara. Sa'an nan ga ku da bin doka da girmama na gaba. Saboda waxannan kyawawan xabi'unku babu shakka Arewa za ta taka rawar gani ba a Tarayyar Nijeriya ba har ma a qasashen "Commonwealth".

Ni da Uwargidana muna taya ku murnar samun mulkin kai, a wannan muhimmiyar rana. Muna kuma aika wa da fatan alheri ga jama'ar Arewa baki xaya tare kuma da yi maku addu'ar Allah Ya Albarkace ku baki xaya."

Firimiya ya amsa jawabin Mai martaba Duke inda ya ce:

A shekaru uku da suka wuce, jama'ar Arewa ta samu girmamawar maraba da Mai martaba Sarauniya da Mai girma Duke of Edihburgh a lokacin da suka kawo ziyara ga wannan jiha. A wannan lokaci ne muka nunawa Mai martaba Sarauniya a cikin mutanen da ke qasashen "Commonwealth" ba mu da na biyu wajen nuna biyayya ga masarautar Ingila da kuma bin Sarauniya sau da qafa. A wannan rana, a kuma madadin jama'ar wannan jiha, ina miqa godiya ga Mai martaba Sarauniya saboda saqonta na fatan alheri tare da nuna farin cikin yadda ta sa ido a kan ci gaban mu da kuma kula da rayuwar jama'armu kamar yadda ta aiko a saqonta.

Bari kuma in juya kan masu Martaba, don in qara cewa a madadin jama'ar wannan jiha muna matuqar farin ciki da maraba da ku. Arewa na yi maku lale marhabin ba don kuna wakiltar Sarauniya ba kawai amma don jin daxin samun wannan dama da kuka baqunce mu. Wannan ranar farin ciki ce a garemu saboda haka muna alfahari da zuwan masu Martaba don su taya mu murna, da jin daxi da annashuwa.

Kamar yadda na cewannan ranar murna da farin ciki ce don haka muka taru muyi bikin samun Mulkin kai, wanda yake da muhimmaci ainun ga rayuwar jama'ar Arewa. Amma bai kyautu in faxi bukukuwa ba kawai sai na haxa da qalubalen da ke gaban wannan jiha. Idan aka kwatanta mu da qasashen da suka ci gaba sai aga muna da muhimman ayyuka a gabanmu. Don kuwa muna tsaka mai wuya ne don bamu yi nisa wajen gina tattalin arziqin qasarmu ba, da kuma fidda ita daga cikin duhun jahilci da cutuka.

Na kan yi tuna ni akan waxannan matsaloli da kuma yadda za a haxa kan mutanen Arewa don gwagwarmayar shawo kansu. Na kan kuma tuna yadda shugaban Ingila Sir Winston Churchill, a wani matsananci hali da qasar Ingila ke fuskanta, shekaru goma sha-tara da suka wuce, amma ya haxa kan jama'arsa ya qwarzanta su ta faxa masu gaskiya, a wannan mawuyacin zamani, tare da kiransu da su zama masu kishin qasarsu da nuna juriya.

Qalubalen da ke gaban Nijeriya, a shekarun 1959 da 1960, kamar na qasar Ingila ce a shekarar 1940. Haka kuma idan muna so mu cimma nasara, to, ya zama tilas mu nuna irin qwazonsu da juriya, da sadaukar da kai waxanda halaye ne da suka ce to 'yanci ga duniya. Na yi imani da, in Allah Ya yarda, jama'armu ba za su yi qasa a gwiwa ba wajen fuskantar qalubalen da ke gabansu.

A baxi, bisa yarjejeniyar da aka cimma a Taron London, tarayyar Nijeriya za ta samu 'yancin kai ta kuma shiga cikin jerin qasashen "Commonwealth". Idan muka kai ga wannan matsayi, za mu shiga cikin qasashe manya da qanana waxanda suke cikin wannan qungiya, za mu kuma riqa tu'amuli da su. Mun kuma yi imani da idan muka nemi taimako ba za mu ci tura ba, za mu sami tallafi amma ba a matsayin mabarata ba amma a matsayin masu tu'amali da juna a bisa tsarin cuxeni-in-cuxeka.

A bisa gudunmawar ta abubuwan duniya da ibada ga "Commonwealth", zan taqaita batu ga Jihar Arewa, zan kuma qara da cewa Ko da yake ita ce Jiha mafi girma, duk da haka tana cikin Tarayyar Nijeriya. Da farko bari in qara faxin abin da kowa ya sani. Arewa na da jama'a masu yawan miliyan goma sha-takwas, ita ce mafi girma bayan qasar Masar a nahiyar Afirka. A fannin gona, muna xaya daga cikin qasashe biyu da suka fi ko'ina aikawa da gyaxa qetare a duniya, mu ne kuma muke aikawa Masaqar Lancashire auduga mafi yawa.

A albarkatun ma'adinai kuwa mu ne muka fi ko'ina samar da duk kuzan nan da ake kira "Columbite" a duniya. Haka kuma muna

xaya daga cikin manyan qasashen da ake samun kuza. A vangaren masaqu kuwa mun fara tasowa ne amma akwai mu da masaqar Kaduna wadda ta fi girma a duk faxin Yammacin Afirka. Wannan ya nuna cewa masaqun mu za su bunqasa sosai in an fara samar da wutar lantarki mai rahusa a cibiyoyin kasuwanninmu. A qasa da shekaru hamsin ne muka sami hanyar jirgin qasa da ta haxa wasu wurare da birnin Kano.

Saboda haka muna iya cewa duk waxannan abubuwan ci gaban an same su ne a rabin qarni, wanda yake kamar xan ba ne a rayuwar qasa. Za mu kuma buxewa abokan tu'ammalin mu babbar kasuwar cinikayya da ke qara girma da hanzari. Haka kuma za mu ba da sharuxxai masu xorewa don yin tabbatacciyar tu'amuli da juna, wanda yake wajibi wajen ci gaban kasuwanci da zuba hannayen jari ingattattu.

Na yi bayani mai tsawo akan kasuwanci saboda alhairan da za a samu a wannan jiha a nan gaba, amma kamar qasar Ingila komai ya ta'allaqa ne akan qwazonmu da xorewar al'amura da kuma bunqasa harkokin kasuwancinmu da duniya. Amma ko kaxan kada a zaci za mu shiga kawance da qasashen "Commonwealth" ne don samun abin duniya kawai. A maimakon hakla kuwa ai harsashin da ke jawo tu'amuli shi ne bin tsari da gaskiya ga al'umma.

A wannan duniya da ke rarrabe, qawancen qasashen "Commonwealth" inda akwai bambacin addini, da jinsi da launin fata da arziqi, rarrabuwa ce da ke da yawan gaske amma sai aka haxa kansu ta hanyar Ibada wadda ta fi ta abubuwan duniya. Haka zalika Jihar Arewa take, jiha ce mai irin waxannan bambance-bambancen amma duk da haka cikin xan qaramin lokaci jama'arta ta haxe ta zama tsintsiya maxaurinki xaya saboda haquri da baiwa kowa 'yancinsa.

Muna tafiyar da zarafinmu bisa gasgata da imani da muka yi da cewa kowane mutum dai-dai yake ga Ubangiji, muna kuma tsammani cewa za mu taka rawar gani in lokacin ya zo ba a tarayyar Nijeriya ba, har ma da "Commonwealth" duk da cewa mu ne za mu zama mafi yarinta a cikin waxannan qasashe. Za mu kuma ba da gudunmawar Ibada ga majalisarta.

A gareku masu Martaba na ke miqa lale da marhabun na jama'ar Jihar Arewa. Wannan Jiha ce mai dadaxxun al'adu waxanda muke tafidda da su da sauyawar zamani. Mun yi qoqari ainun wajen kare martabar al'adunmu a shekarun baya, za mu kuma ci gaba da yin haka a nan gaba. Muna masu riqo da xabi'u da

al'adunmu na gargajiya masu kyau da kuma daukar sabbi na zamani don mu murje su ta amfani da sabbin hanyoyin amfani da ilimi da fasaha. Ta haka ne za mu taka rawar gani a wannan sabuwar duniya.

A cikin al'adun da muka gada daga iyaye da kakanni, muke kuma son mu koyawa 'ya'yanmu babu kamar bi da girmama hukuma. Saboda wannan al'adarmu ba mu ko shakka za mu ci gaba da havaka kamar yadda muka yi a shekarun baya. Haka kuma xabi'u da makarantunmu, namu ne na asali, ba aronsu ko kwaikwayonsu muka yi ba a wannan zamani.

Al'adunmu Ko da yake sun daxe da kafuwa amma suna tafiya da zamani kamar yadda ya dace don haka ne suke qara girma da havaka. Muna kuma alfahari da irin hali da tsarin rayuwar mu, muna kuma farin ciki da samun muhimmiyar dama da za mu nuna kaxan daga cikinsu. Muna kuma fata masu Martaba za su ji daxin ziyararsu ga wannan jiha, in kuma sun gama, muna fata Ubangiji ya maida ku gida lafiya.

A cikasawa, zai dace da in yi tsokaci a kan Mai martaba Sarauniya. Ita ce alamar da ta haxa kan qasashen "Commonwealth" duk da bambancinsu, ta kuma cusa xa'a da martabar 'yan'uwantaka domin ciyar da 'yan-Adam gaba. Don haka muke ba ta daraja da martaba a wannan jiha. Saboda haka muke roqon masu martaba da su isar da saqon gaisuwar jama'ar Jihar Arewa ga Mai martaba Sarauniya da kuma fatan Allah Ya ja zamaninta, ya bata tsawon rai da jin daxi. Da kuma fatan zata qara ziyartarmu ba da jimawa ba."[1]

Qasaitacciyar Liyafa

Ziyarar masu Martaba ta yi armashi qwarai da gaske. Baqi da 'yan gari duk cike suke da farin ciki. 'Yan Arewa na murnar samun mulkin kan jiharsu. Su kuma baqi na godiyar zuwan su wannan shagalin bukin samun mulki. 'Yan Arewa ba su da na biyu wajen karrama baqi ballantana manyan baqi daga Masarautar Ingila. A dalilin haka ne Firimiya Sir Ahmadu Bello mai masaukin baqi ya shirya wata qwaqqwarar liyafa. Sunayen waxanda suka halarci wannan liyafar sun haxa da: Sir Ahmadu Bello, da Malam Isa Dutse, da Duke da Duchess, da Sir Gawain Bell, da Lady Bell, Miss Holland (Lady in Waiting), da Major Hawkins, da Mr. A.C. Mackellar.

[1] NC, Asabar, 16/5/1959, shafi na 4

Akwai, Mr. Alan Lennox – Boyd, da Lady Patricia Lennox Boyd, da Mr. A.T Weatherhead, da Sir Algernon Brown, da Lady Brown, da Mr. H.H. Marshall, Q.C., da Mr. H.A.S Johnston, da Mrs. Johnston, da Mr. W.E Rumbelow, da Mrs Rumbelow, da Brigadier Young da Uwargidansa, da Sir Bryan Sharwood-Smith da Uwargidansa.

Aqwai kuma, Earl De La Warr, da Mr. S.J. Hogben da Uwargidansa, da Sir Sidney Phillipson, da Hon. Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa, da Cif. Hon. Awolowo da Uwargidansa, da Dr. Nnamdi Azikiwe, da Mr. Kapur, da Mr. J.B Davies da Uwargidansa, da Major Farinton da Uwargidansa da Mr. W. Baemur, da Air Vice Marshall Walker, da Alhaji Abdulmaliki Ata, da M. Abba Jiddum Gana, da Lord Colyton, da Mr. Fenton da Uwargidansa, da General Sir Frank Simpson, da Mr. J.C Whittaker da Uwargidansa, da Mr. E.I. Oliver, DSO, O.B.E., T.D., da Uwargidansa, da Mr. W.T.G Gates.

Tun kafin jihar Arewa ta sami 'yancin kanta shugabanninta sun yin namijin qoqari wajen qulla zumunci tsakanin qasar Ingila da wannan jiha mai maxaukakiyar daraja. A wancan lokacin idon duniya duk na kan Arewa ne domin ita aka sani, ita ce Nijeriya xungum. Akwai hulxa mai kyau wadda ta share wa 'yan Arewa qofar shiga qasar Ingila ta kowace qofa a kuma kowane lokaci. Saboda haka ne 'yan Arewa suka fara jerin gwano zuwa qasar Ingila musamman don neman qarin ilimi a fannoni daban-daban. A hankali kuma za su riqa zuwa qaro ilimi mai zurfi sosai.

Kafin farin ciki da murnar samun mulkin kan jihar Arewa su kwaranye sai ga batun shagulgulan samun 'yancin Nijeriya sun taso. A wannan lokaci ma idandunan qasashen duniya a kan Arewa suke. Da yawa daga cikin waxannan qasashe na zakwaxin zuwa waxannan shagulgula ne saboda jihar Arewa wadda ta yi suna wajen nuna kara, mutunci da halin girma. A wannan lokaci ne Firayim Ministan Ingila Mr. Harold MacMillan ya ce shi zai fara shigowa da qafar dama.

KASHI NA GOMA SHA-TAKWAS

'Yancin Nijeriya

Ziyarar Wazirin Ingila

A safiyar ranar Sati 16 ga Janairu shekarar 1960, da qarfe goma da minti ashirin na safe, Firayim Ministan Ingila Mr. Harold MacMillan tare da Uwargidansa za su sauka Kaduna daga Jihar Gabas. gwamnan Jihar Arewa Sir Gawain Bell da Uwargidansa, da Firimiyan Jihar Arewa Sir Ahmadu Bello, da Ministoci da kuma sauran manyan mutane za su tarye su. A ran nan dai Mr. MacMillan zai sadu da Firimiya da Ministocinsa a xakin taro na Nasarawa. Da Yamma Firimiya zai raka shi ya ziyarci *Lugard Hall* inda zai sadu da Shugaba da Akawun Majalisar. Daga nan kuma zai yi kallon wasan qwallon hannu, sai kuma ya ratsa Kaduna zuwa Masaqar Kaduna. Bayan ya koma masauki a gidan Gwamna ya xan shaqata, da qarfe bakwai da kwata na dare zai halarci wata qasaitacciyar liyafa da Firimiya ya kira a sabon gidansa.

Ita kuma Uwargidansa, Lady Dorothy a wannan rana za ta ziyarci makarantar da 'ya'yan Baqar Fata da na Turawa ke haxe wato *Capita School* da kuma Makarantar Koyon Aikin Jiyya. Uwargidan Gwamna ita za ta raka ta wajen wannan rangadi. Ran Lahadi, Firimiyan Jihar Arewa zai raka babban baqonsa zuwa Zariya ta mota. A mil na bakwai zuwa Zariya za su haxu da Sarkin Zazzau da Razdan. A kan hanyarsu ta zuwa fadar Sarki za su haxu da masu dawaki xari uku sun yi banga-banga kan hanya. Kafin dai Mr. MacMillan ya koma Kaduna ta jirgin sama a ran nan zai ziyarci Makarantar Koyon Aikin Mulki, kuma yaci abincin rana a gidan Razdan. Haka dai aka bi wannan shiri na Babban Baqo daki-daki kuma bisa tsari.

Ran Litinin da safe, Mr. Macmillan da Uwargidansa za su koma Ikko. In sun xan shakata, sai su shiga jirigin sama zuwa Salisbury. A ranar da Mr. Macmillan ya isa Ikko daga Ghana sai da ya yiwa haxaxxen taron Majalisar Wakilan Nijeriya da ta Senate jawabi ran Laraba. Cikin manyan mutanen da suka halarci kallon wannan haxaxxen taron a ranar da Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello da waxansu Sarakuna uku daga Arewa da waxansu Ministocin Arewa goma sha-xaya da suka je Ikko musamman.

Cikin jawabin maraba da Firayim Ministan Nijeriya Sir Abubakar ya yi wa Mr. MacMillan, ya ce mutanen Nijeriya suna murna da ya ziyarci Nijeriya a farkon Shekarar tunawa da samun 'yanci. Mutanen Nijeriya kuma suna godewa

Mr. MacMillan kan sha'awarsa ga kasancewar siyasa da shirin mulkin Nijeriya nan gaba.[1]

A zuwansa Arewa an yi masa qasaitacciyar liyafa. A wannan liyafarce Firimiya ya yi wannan jawabi:

> *Mai girma Mr. MacMillam, maza da mata. Wannan itace ziyarar farko da wani Firayim Ministan Ingila ya yi zuwa Jihar Arewa, saboda haka take da muhimmanci qwarai da gaske. Ina kuma mai matuqar farin ciki maraba da lale, a madadin gwamnati da jama'ar wannan jiha da zuwan Mai girma Mr. Harold da Uwargidansa Lady Dorothy MacMillan.*
>
> *A cikin watanni tara da suka wuce, mun qarbi ziyarar Ministocin Mai martaba guda uku, wato Mr. Lennox-Boyd wanda ya zo a watan Agusta sai a yanzu ga Firayim Minista. Ina fata za mu samu qarin irin wannan ziyara saboda zata qara danqon zumunci tsakanin waxannan qasashe biyu. Haka kuma bana shakka ko kaxan ministan da zai kawo ziyara a nan gaba, zai zama Scot ne wato, mutumin Scotland.*
>
> *Mutanen Scotland ana maraba da su a ko yaushe a Jihar Arewa saboda mun xauke su a matsayin 'yan Arewa ne mazauna Ingila. Don haka bana mamakin yadda suke riqe manyan muqamai a Ingila. A kwanan baya ne wannan babban baqo ya shiga harkar siyasa wadda mulkin Dimukuraxiyya ta kawo wato babban zave. Ni, kaina na shiga cikin zaven Tarayyar da aka yi a nan. Saboda haka ina iya cewa dukkanmu mun goge sosai mun kuma kai ga nasara. Haka zalika masu ra'ayin Mazan-Jiya ne suka yi nasara a zaven da aka yi a Ingila, masu ra'ayin mazan-jiya su ne suka yi nasara a zaven da aka yi a Nijeriya.*
>
> *In Allah Ya yarda, ran 1 ga watan Oktoba, za mu samu 'yancin Kai. Ba a samu a tarihi ba, wata qasa dake qarqashin Mulkin Mallaka, wadda ta ci gaba har ta kai ga samun 'yancin kai cikin hanzari da lumana. Don haka ya wajaba mu gode wa jama'ar mu wajen nuna juriya da hikima da suka yi. Ya kuma zama wajibi in yi godiya ga gwamnatin Ingila saboda hangen nesanta tare da biyayya da sadaukar da rai da ma'aikata 'yan Nijeriya da baqi da suka nuna.*
>
> *Ina mai goxiya ta musamman ga ma'aikata 'yan qasashen waje saboda biyayyar da haxin kai da suka bayar, da kuma fatan za su ci gaba da yin haka a nan gaba. Abu ne mawuyaci ma'aikata su sauya*

[1] GTK Ta 937, Jumma'a 15/1/1960

halayensu daga tsarin mallaka zuwa ga tsarin 'yanci, amma wannan sauyi ba zai yiwu gaba xaya ba. Amma idan aka samu kyakkyawar manufa ga dukkan ma'aikata, ina ganin za a samu sahalewa da haxin kai a tsakanimu a lokaci mai zuwa. Na sani na kan zama mai tsawartawa a wasu lokuta, amma ai idan shugaba ba ya tsawartawa ba za a samu aiki da gaskiya ba, amma duk da haka ba na nufin in qwamamawa kowa ba ne ko kuma yin bita da qulli. Na kuma san akan manta da gazawar qalilan amma nasarorin kasiran kuwa ba za amanta da su ba har bayan ransu. Buri na ne in ga ma'aikata Turawa da suka tsaya baya sun yi aikin da zai qara danqon zumunci da qasar Ingila, za su kuma guje wa duk wani abin da zai kawo cikas a dangartakar da ke tsakaninmu.

Yallavai, ka yi mani alfarmar isar da saqon godiyar Nijeriya ta Arewa ga Mai martaba Sarauniya saboda sha'awarta ga harkokinta tare da dattakun da gwamnatinta ta nuna wajen jagorancin wannan qasa ga kaiwa ga samun 'yanci. Muna kuma da burin ba da tamu gudunmawa da kuma taka rawar gani, a matsayinmu na 'yantacciyar qasa mai cin gashin kanta kuma xaya daga cikin qasashe masu qawancen Ingila wato "British Commonwealth of Nations". Saboda mun yi tarayya wajen manufofin wannan qungiya, muna kuma masu alfahari da shiga cikin wannan babban 'yan uwantakar al'ummomi.[1]

Firayim Ministan MacMillan ya amsa jawabin Firimiya, inda ya ce:

Ina farin ciki da samun wannan dama na yi na ziyarar Jihar Arewa. Yallavai, ni da uwargidana muna masu matuqar godiya gare ka, saboda ka karve mu cikin farin ciki da faraga. Ina kuma shaida maka naji daxi da kace ka samu taimako da agaji daga Turawan Ingila waxanda suka nuna maka biyayyarsu wajen aiki. Yallavai, ba zan kasa isadda saqon ka ga Mai martaba Sarauniya ba wanda nauyi ne ka xora mani.

Haka zalika, ina farin cikin ganin xan Arewa naiwa xan Arewa lale da marhabin. Kamar yadda kace ne muna da abubuwa da dama da suka kamanta mu, alal misali, mu 'yan Arewa a Ingila na iya zama masu amfani gare ku. A Ingila a yau, mu 'yan qabilar Scot saboda nuna fifiko da mu ke yi kan jawo mana so da kwarjini, wataqila ma har da hadasa amma duk da nuna bambanci muna aiki cikin haxin kai da 'yan Kudu wajen cimma manufa. A wasu lokuta ma auratayya na

[1] NC, Laraba 20/1/1960.

qara haxin kai a tsakaninmu. Yallavai, ina farin ciki ta yadda ka yi maraba da uwargidana wadda ita 'yar Kudu ce.

Kamar Scotland, Jihar Arewa ta bambanta a tarihi da al'adu da Kudu maqwabciyarta. Amma na tabbata da yake lokacin samun 'yanci na qaratowa za a a riqa samun qarin qarfin aminci da fahimtar juna tsakanin waxannan jihohi. Amma duk da haka kada aminci da fahimtar juna su taru su share halayen kowace jiha. Yallavai, wannan zai sa al'ummar Nijeriya, su riqa magana da murya xaya, har ila yau haxin kan jama'ar ne zai qara qwarzanta qarfinta, a cikin qasar harda qasashen waje.

Ko da yake ziyarata zuwa wannan qasaitacciyar qasa na xan qaramin lokaci ne. Amma na yi 'yan kwanaki a Ikko hedkwata, ba kuma zan manta da gagarumin bikin da aka yi mani ba inda kai, yallavai, da abokanka masu yawa suka halarta.

Wannan rana ce ta tarihi, amma duk da haka sai da na buqaci ganin wasu abubuwa a sauran jihohi. A wannan ziyarata a Arewa cikin xan qaramin lokaci naga abubuwa fiye da abubuwan da na gani a hedkwatar ku. Haqiqa wasu manyan gine-ginen ku masu kyau sun bani sha'awa kamar Sabuwar Babbar Kotu wato "New High Court", wanda kyakkyawar husumiyarsa ta miqe sama kamar naman-kaza wato mushroom. Haka kuma Gidan Shawara (Lugard Hall) da Ofishin Kantoma wato "Administrative Buildings", da wannan kyakkyawan waje da muka haxu a wannan dare duk gine-gine ne masu qawatarwa da ban sha'awa.

Ina so kuma inga bunqasar masana'antu a Kaduna musamman Masaqar Kaduna. Gobe, ina so na ga birnin Zazzau mai tsohon tarihi tare da abubuwan gargajiya masu ban sha'awa. Ina fata in ga makarantu da wuraren havaka ilimi, a can.

Duk abubuwan nan da na gani, manyan gine-gine masu qawatarwa, da kamfanoni da kuma son girma da ci gaba, alamomi ne na qaratowar samun 'yanci. Ina kuma farin ciki da samun daman ganin su, amma na sani sosai ci gaban Al'umma na ainihi, ya dogara ne a kan yawan jama'ar Karkara da arziqinta waxanda suka kafu a kan masana'antu tare da saye da sayarwa.

Kamar yadda ka ce, Nijeriya ta nuna misali fitaccewajen ci gaba ga kai wa ga samun 'yanci ta haxin kai tare da kyakkyawan niyya. Babu kuma inda akaga haka zahiri kamar Jihar Arewa, inda tsarin Mulkin gwamnati irin samfurin da Lord Lugard ya fara gabatarwa, "domin", kamar yadda ya ce a kalaminsa kamar haka: "a jama'ar su girmama shugabaninsu su zama masu alfahari da al'adunsu waxanda

za su kira na su ne asali." Waxannan kalamai cike da hikima da suka zama harsashi mai qarfi akan bisa wannan harsashi mu da ku, muka haxu muka dasa shikashikan 'yancin mutum da juriya, waxanda da su ne ake gina al'umma mai xorewa wadda zata girma ta bunqasa.

"Wannan shi ne ziyarata ta farko ga qasaitacciyar qasarku. Ina fata kuma ba itace ta qarshe ba. Yallavai, bayan babban zave mai zuwa, ina fata zaka zo London don ka ganmu, zan yi qoqarin in mayar maka da ziyara zuwa nan. Duk da haka mun san juna cikin 'yan shekarun nan. A cikin waxannan shekaru na qarshe, a tafiya zuwa ga matakin qarshe, Nijeriya a shaqu da Manyan Sakatarori, wato Lord Chandos da Mr. Lennox – Boyd. Na yi farin ciki da naji kai masu godiya. Yallavai, abokanku masu kyau sa'anan abokan Ingila ne, na yi imani da cewa za a daxe ana tunawa da su.

Zan baka tabbacin cewa, a waxannan mawuyacin shekaru da ke tafe, ni da abokan aikina a Ingila, za mu ci gaba da sa ido ga ci gaban ku tare da tausayi da fahimta. Ni kuma abubuwan da naji na kuma gani, a wannan gajeriyar ziyara mai muhimmanci sun qara mani qaimi. Yallavai, Ina fata kamar yadda kake fatan ganin Nijeriya zata taka rawar gani a qungiyar "Commonwealth".

Akwai qalubale da dama masu yawa da ke buxe da lokaci mai zuwa. Na yi imani da taimakon Ubangiji za ka yi amfani da waxannan dama ka fuskanci qalubalen. Sai an jima.[1]

Ko shakka babu a duk qasashen da ke qawance da Ingila, Nijeriya ta Arewa bata da na biyu wajen nuna biyayya ga Sarauniya. Koda Mai girma Wazirin Ingila ya kawo ziyara Nijeriya, bai gamsu ba sai da ya kai ziyara ga gidan sarauta a Arewa. Irin karimcin da Sarakuna ke nuwa manyan baqi daga Ingila ya taimaka gaya wajen qara danqon zumunci tsakanin qasar Ingila da Nijeriya ta Arewa. Saboda haka ne Wazirin ya kai ziyara ta musamman Zariya.

A ranar Lahadi 17 ga Janairu, Firayim Ministan Ingila da Uwargidansa suka kai ziyara birnin Zazzau. Firimiyan Arewa ne ya yi masu rakiya, shi kuma Mai girma Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu ya taryesu a waje mil bakwai kafin isa Zariya. Daga nan aka tafida manyan baqi zuwa fadar Zazzau, inda aka yi masu wasan dawakai tare da kaxe-kaxe da raye-raye na gargajiya masu ban sha'awa.

Daga nan sai babban baqon ya ziyarci Makarantar Koyon Mulki, wato *Institute of Administration*, inda ya duba sashe-sashe na wannan makaranta, ya kuma sadu da malamai da ma'aikatan makarantar. To, hankalin babban baqo ya

[1] NC, No. 804 Laraba 20/1960, shafi na 12

kwanta don ya zo Arewa ya ga karimci da girmamawa, da nuna qasaita da ga shugabanni, da Sarakuna da jama'ar wannan jiha mai bambanci da ban mamaki. Bayan haka ne sai baqo zai yi halinsa, zai koma gida. Firayim Minsta, ya yiwa qasa jawabi da Yamma a ranar lahadi 17 ga Janairu inda ya ce;

Kwana shida da suka wuce ne, ni da uwargidana muka iso Ikko, inda na ce da Firayim Ministan ku ban zo domin yin magana ba amma don in saurara, in fahimci matsaloli da burin Nijeriya. Gobe da asubahim fari zan tashi zuwa sauran wuraren da ke qawance da Ingila.

Zan tafi da abubuwan tunawa masu yawa na mutane da suka yi kan gaba wajen nuna kara, da so da qauna da kuma kyautatawa. Zan tafi ina tunanin qasa mai alfahari da al'adunta; da kuma shugabanni da suke da qwazo da azama wajen ciyar da da qasarsu gaba, da raya qasa da jin daxin jama'arta. Zan kuma koma ina tunawa da haxaxxiyar da kuma tabbatacen imani da ci gaban Nijeriya a nan gaba.

Muna masu farin-ciki ainun da karamci da kuka nuna mana a duk inda muka ziyarta, ci gaban da kuka yi da na gani ya bani sha'awa matuqar gaske. Na samu tattaunawa da Firayim Ministan ku da Firimiyoyin jihohi na lokaci mai tsawo, na yi imani da cewa a qarqashin shugabancinsu, Nijeriya za ta cimma manufa a shekarun da ke tafe.

Zan kuma koma da alfahari da jin cewa mutanena suna taimaka wa gaya suna kuma taka rawar gani a yanzu wajen gina wannan qasaitacciyar qasa. Na yi matuqar jin daxi da godiyar shugabanninku da suka yi wa Turawa maza da mata 'yan qasar Ingila don gudunmawar da suka bayar da kuma sauran mutane daga sassan qungiyar "Commonwealth.

Ina mai matuqar godiya gareku duka, mun yi ziyara mai ban mamaki. Allah Ya Albarkace ku a shekaru da ke tafe.

Ko da yake Wazirin Ingila bai daxe ba a lokacin da ya kawo ziyara wadda ya ce tana da ban mamaki amma kamar sauran ziyarorin manyan shugabannin Ingila ta qara danqon zumunci tsakanin Ingila da Nijeriya ta Arewa. A sabili da haka ne da zai koma gida sai jama'ar Arewa ta ce da shi, adabo!

Mr. Harold MacMillan, Firayim Minstan Ingila da Uwargidansa Lady Dorothy, sun gama ziyarar da suka kawo Arewa ta kwana biyu a ranar Litinin 18 ga Janairun shekarar 1960. A safiyar wannan rana ce manyan baqin suka tashi daga filin jirgin saman Kaduna zuwa Ikko, a matakin farko na tafiyarsu zuwa

Salisbury ta qasar Kudancin Rhodesia. gwamnan Arewa Sir Gawain Bell, da Firimiyan Arewa Sir Ahmadu Bello tare da 'yan Majalisar Zartaswa ne, suka yi masa rakiya zuwa filin jirgin saman Kaduna, a inda suka ce da shi Adabo, sai wata rana.

Wannan Babban Baqo sai ya zama tauraron da ya haskaka shekarar 1960 wadda kowa a Nijeriya ke murna da shigowarta. Shekara ce kuma da ta zo da qalubale masu yawan gaske.

A lokacin da Nijeriya ke xingisawa zuwa ga samun 'yanci ne Mai girma Hugh Anthony Stephen Johnston Esq, C.M.G., O.B.E., D.F.C., ya riqe matsayin gwamnan Arewa mai riqo. A lokacin da ya riqe wannan muqami ne, ya yi jawabi ga Majalisar Sarakuna ran 4 ga Mayu 1960. Ga jawabinsa:

Shugaba, Sarakunan Jihar Arewa:

Abin farin ciki ne da na sami wannan dama in yi muku jawabi a qarshen shekarar farko ta Mulkin Kan Jihar Arewa kuma lokacin da Nijeriya baki xaya ke gab da samun cikakken 'yanci, in kuma bayyan maku muhimman shirye-shiryen da gwamnatina ke yi saboda qarin ci gaba na Jihar nan cikin shekara mai zuwa.

Za a sake roqon ku ku duba istimat na Kuxin Shiga dana Kashewa na shekara ku kuma yarda da kuxin da gwamnatina za ta kashe wajen tafiyar da shirye-shiryenta na shekara mai zuwa da na riqe aikace-aikacenta na yau da kullum. Saboda watan Azumi majalisun Dokoki ba su iya qare duba istimat xin ba sai da aka yi makwanni bayan shigowar shekarar kuxi. Saboda haka Ministan Kuxi ya yi aiki da ikon da Dokar Mallaka da Tafiyar da Kuxaxen gwamnati ta bashi, kuma ya ba da izinin kashe kuxi da suka zama wajibi don tafiyar da aikace-aikacen Qasa kafin Majalisun Dokoki su yarda da Dokar Kasafin Shekarar. Wannan Doka za ta tanadi kuxin kashewar yau da kullum na kusan £18,000,000 saboda shekara mai zuwa. Ban da wannan kuma an shirya istimatin Manyan Ayyuka da za a kashe kusan £10,000.000.

Istimatin ya yi lissafi da qarin tanadin da a ke buqata saboda biyan qarin albashi da Kwamishan Mbanefo ta yi wadda gwamnatina ta yarda da shi. Ministan Quxi zai gabatar da wata doka da za ta yi izinin karvar rancen £2,000,000 wanda gwamnatin Mai Alfarma ta Ingila ta baiwa Jihar nan.

Cikin aikace-aikacen yau da gobe na gwamnatin nufin Ministocina ne su ci gaba da kyautata sha'anin lafiya, arziqi da zaman jama'armu ta kowace hanya.

Da taimako daga waje an yi nufin a yi binciken arziqin qasar Jihar nan, a kuma yi binciken hanyoyin da a ke shirya tafiyar da ma'aikatun Ministan Aikin Gona da Ministan Lafiyar Dabbobi da Aikin Daji.

gwamnatina tana fatan wannan bincike zai jawo tattara qarfi da qara kyautata albarkar qasarmu.

Ma'aikatar Aikin Gona za ta qara buxaxa harkokinta a qara qarfafa aikace-aikacen Lafiyar Dabbobi kan manyan cutuka, amma Ma'aikatar Ministan za ta ci gaba da ayyukanta da ta saba yi. Za a qara maida hankali kan buqatun Fulani masu kiwo.

Za a kuma qara buxe aikace-aikacen ilimi cikin dukkan Jihar nan da gaggawa yadda zai yiwu. An yi shirin buxe sabbin makarantun Sekondare goma cikin shekarar 1960, kuma za a mayar da azuzuwan makarantu biyu su riqa tafiya azuzuwa biyu biyu. Ana kuma fata shirin nan na baiwa yara duka ilimin Firamare da aka fara a Kano za a buxe shi a waxnsu wurare. Za a yi shawara a kan kyautata matsayin Makarantun Alqur'ani.

gwamnatina za ta ci gaba da manufarta ta danqa wa 'yan Arewa jagorancin Arewa.

Ana nan ana gina, ko kuma sake gina asibitoci bakwai a Azare, Bama, Birnin Kudu, Ganye, Hadejia, Okene da Wukari. Kuma kwanannan za a fara ginin sabon asibitin Kaduna.

Ma'aikatar Ministan Lafiya za ta ci gaba da ba da qoqari wajen koyar da ma'aikata na kowace daraja da muqami. Kuma za a ci gaba da buxaxa ayyukan lafiya a qauyuka.

gwamnatina za ta ci gaba da watsa labaran qoqarinta kan ayyukan raya qasar Jihar nan, a gida da kuma qasashen waje. Ma'aikatar Watsa Labarai ta Jiha, za a sake mata shiri da tsari. Ana duba yiwuwar kawo rediyo mai hoto (television) a Kano, Zariya, Kaduna da kewayensu.

Ana fata nan gaba ba da daxewa ba a gabatar da sabuwar Dokar Qasa da Mallakar Qasa.

Kwanan nan aka gama shirya Qa'idodin Zave na Majalisun Larduna, kuma ba da daxewa ba Majalisun za su soma aiki.

gwamnatina ta yarda da irin muhimmin aikin da En'e-En'e su ke yi wajen mulkin Jihar nan kuma za ta taimakesu ta kowace hanya cikin qoqarinsu na su kyautata ayyukansu don su dace da zamani da kuma aikinsu na mulkin garuruwa da qauyuka.

A bara ya zama dole a kafa kwamitocin Bincike kan al'amuran waxansu En'e-En'e, kuma abin da aka tarar a xaya daga cikin

binciken nan ya sa wani daga cikin mashawartan majalisan nan ya yi murabus. gwamnatina har abada za ta tsaya sosai ta ga an yi gaskiya da adalci cikin al'amuran En'e-En'e kuma ko yaushe za ta yi abin da ta ga ya wajaba don ta kai ga wannan manufar. gwamnatina dai ta amince da cewa dukkan Sarakuna nan gaba za su riqe jama'arsu bisa gaskiya da adalci kamar yadda yawancinsu ke yi a ko yaushe.

Kamar yadda kuka sani aan kafa sabon mulki a Kamaru ta Arewa saboda quri'ar nan ta kwanan baya da aka yi. Daga ranar 1 ga watan Oktoba, ranar da Tarayyar Nijeriya za ta sami 'yanci za a raba qasar amana ta Kamaru da Nijeriya kuma za a naxa Kantoma daga gwamnatin Sarauniyar Ingila wanda zai riqe qasar. Za a yi quri'a ta biyu wajen watan Fabarairun shekarar 1961 lokacin da za a tambayi mutanen qasar waxannan tambayoyi biyu:-

(a) Kuna so ku sami 'yanci ta haxuwa da 'yantacciyar Jamhuriyar Kamaru (wato Kamaru ta Faransi wadda ta sami 'yanci)?; ko
(b) Kuna so ku sami 'yanci ta haxuwa da 'yantacciyar Tarayyar Nijeriya?

Qaruwar lalacewar yara ta zama abin damuwa don haka ana sake qoqarin maganin wannan ta qarfafa En'e-En'e da basu riga sun xauki, malaman tarbiyya ba, su kyautata kuma su qara Gidajen Tsaron Yara da Makarantun Gyaran Hali, kuma su qarfafa kafa Kulob-kulob na Samari da wasanni. Za a duba shawarwari kafa wata Hukumar Wasanni ta Jiha.

Za a yi kowane irin taimako ga raya sana'o'i ko ina cikin Jihar nan kuma gwamnatina ko yaushe za ta yi na'am da jari daga qasashen qetare.

Cikin Shirin Raya Hanyoyi na shekarun 1960 – 61 an shirya a gama hanyoyin Argungu zuwa Birnin Kebbi zuwa Jega, Bunga ta Ningi zuwa mahaxar babbar hanyar nan A21 ta cikin lardin Kano, Kauran Namoda zuwa Jibiya, sashi na biyu na Kano zuwa Gumel zuwa Hadejia da sake gyara hanyar Bokani-Bida-Keffi-Gudi zuwa Akwanga.

Bara gwamnatina ta gabatar da mataki na farko na sake tsarin dokoki da shari'o'i da Qungiyar Alkalan nan ta ba da shawara ta kawo Dokar Tsarin Hukumcin Laifi gabanku. A wannan shekarar gwamnatina za ta cikasa waxannan shirye-shiryen da Shirin Dokoki da ba su kasa tara ba, mafi tsawonsu shi ne, Tsarin Hanyar Hukumcin Laifi. Lokacin da Tsarin Hukumcin Laifi da Tsarin Hanyar

Hukumcin Laifi. Lokacin da Tsarin Hukumcin Laifi da Tsarin Hanyar Hukumcin Laifi tare da sauran Dokokin Tarayya da ke haxe da waxannan suka soma aiki za a sami shari'ar Laifi a Jihar nan wadda za a riqa amfani da ita a Babban Kotu, Kotunan Majistare da duk Kotunan Qasa.

Zai zama wajibi kuma a kafa sabbin Kotuna biyu, su ne Kotunan Xaukaka Qarar shari'ar Musulumci da Kotun Warware wa, da ke da sabuwar hanyar xaukaka qara daga Kotunan Qasa. Za a kafa wani sabon Kotun Qasa da za a kira Kotun Lardi a kowane Lardi. A qarshe tsofaffin Kotunan Majistare masu ikon shari'ar laifi da na haqqi za a rushe su kuma nan gaba Majistarori za su sami ikon yin shari'ar laifi ne kurum, ikon su kuwa kan shari'ar neman haqqi zai koma wani sabon Kotu da za a qira Kotun Gunduma.

An kafa wani Kwamiti da zai baiwa gwamnatina shawara kan aikin Di'o-Di'o cikin sabbin shirye-shiryen gwamnati da na ma'aikatanta da suke qaruwa a Jihar nan. Lokacin da Kwamitin nan ta ba da rahoto za a duba maganar yin waxansu canje-canje da gyare-gyare cikin aikace-aikacen da aka ga sun dace saboda canje-canjen shirin Mulki.

Na sani ku Sarakunan Jihar nan za ku ci gaba da ba da bukkan qoqari, wajen kyautata zaman jama'arku a shekaran mai zuwa. Kuma ina roqon Allah Ya taimakeku ya nuna haske cikin wannan babbar manufa.[1]

Wannan gajartaccen jawabin Gwamna mai riqo, Mai girma Hugh Anthony Stephen Johnston, ya haskaka kyawawan manufofin gwamnatin Jihar Arewa a shirinta na samun yancin Nijeriya. Akwai abubuwa muhimmai da Gwamna ya bayyanar kamar: faxaxa baiwa yara duka ilimin Firamare da aka fara a Kano, da kyautata matsayin Makarantun Alqur'ani, da danqawa 'yan Arewa jagorancin Arewa, da Aikin Gona.

Waxannan buqatu nada daga cikin manyan manufofin gwamnatin Jihar Arewa wadda Sardauna ke wa jagoranci. Da waxannan manufofi ne Arewa ta fuskanci samun 'yancin kai a watan Oktoba na shekarar shekarar 1960. Babu shakka kowa zai shaida cewa Sarakunan Arewa sun taka rawar gani a wajen cimma waxannan manufofi da makamantansu. A dalilin haka ne ma Gwamna Johnston ya yiwa Sarakuna jinjina, inda ya ce: "gwamnatina ta yarda da irin muhimmin aikin da En'e-En'e su ke yi wajen mulkin Jihar nan . . ."

---

[1] AH/SA/A4 - 2

Gari ya Waye Safiya ta yi

Nijeriya ta kai ga samun 'yanci tana tafiya a shagixe saboda kasancewar baraden yaqin neman 'yancin sun yi yaqin ne ba a qarqashin tuta guda ba. An kuma samu bambancin ra'ayi a lokacin da wannan qasar za ta samu 'yanci. Kudu na cewa a bamu lokaci ya yi, Arewa kuwa cewa take, a saurara a bani lokaci ban shirya ba. Da haka aka kai. Da qyar na kai, ya fi da qyar aka kama ni.

Nijeriya ta ga tsarin mulki iri-iri kafin ta cimma muradinta. An baiwa Nijeriya yanci a shekarar 1959 wanda zai fara aiki a ran 1 ga watan Oktoban shekarar 1960. A wannan rana ce aka shirya gagarumin biki a Kaduna. An yi wannan biki a filin sukuwa wato Murtala *Square* don taya Nijeriya murnar Samun 'yanci. Garin Kaduna ya cika maqil da jama'a waxanda suka zo daga sassa dabam daban na Arewa da sauran jihohin qasar nan. Akwai kuma mutane masu yawa da suka zo daga qetare don su taya 'yan Nijeriya murna da wannan rana.

A wannan rana ce Firayim Ministan Nijeriya, Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa ya yi wannan jawabi ga jama'ar Nijeriya ya ce:

"Jama'a yau babbar rana ce, ko da yake ba kullum mu ke tare da ku ba, amma kowane lokaci kuma kuna cikin zukatammu. Yau ranar Samun 'yanci. Dukammu waxanda Allah Ya sa muka ga wannan rana ta yau, wajibi ne garemu, mu gode wa Ubangijimmu Allah, mu yi addu'a Allah Ya sa wannan sakewar hijira da ta fara a yau, ta zama alheri ne ga dukkan jama'ar qasar nan maza da mata. Tafiyar da mulkin qasa abu ne mai wuya, tum ma ba a yau ba, amma idan dukammu muka yi niyya, muka sa tsoron Ubangiji cikin zukatammu za mu kai ga nasara. [1]

A wannan rana ce kuma Firimiya, Alhaji Sir Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato, ya aika da wayoyin taya murna, da fatan alheri ga wasu muhimman mutane. Sardauna ya aika wayar fatan alheri ga Cif Awolowo, Shugaban Jam'iyyar Action Group da Uwargidansa, wadda ta ce: "Babbar fatan alheri zuwa gareka bisa samun 'yancin Nijeriya. Ina fata Allah zai taimake mu duka don yin abin da zai amfani mutanenmu. "Ya aikawa Malam Aminu Kano, Majalisar Wakilai Ikko da wannan saqo:

"Babbar gaisuwa zuwa gareka da Majalisa kan samun 'yancin Nijeriya. Ina roqon Ubangiji cewa a ko yaushe shawarwarin Majalisa za su tsaya kan abin da zai amfani Nijeriya da mutanenta."

---

[1] GTK 7/10/1960, shafi na 8

Firimiya ya aika da irin wannan saqo (a sama) ga Shugaban Majalisar Nijeriya, Ikko, da Shugaban Majalisar Wakilai, Enugu; da Shugaban Majalisar Sarakuna Ibadan da Shugaban Majalisar Sarakuna, Enugu.[1]

Garin Kaduna kuwa ya cika da mutane maqil ana shagulgula da bukukuwa iri-iri, abin sai wanda ya gani. Shugabannin qasashen waje da suka hallara a Kaduna Hedkwata suna da yawa. Akwai wakilan qasashen Turawa da Larabawa da na qasashen Afirka da Asiya duk sun hallara a wannan gari. An kuma samu saqonnin shugabanni ta wasiqu da wayar tarho da dama. A wannan rana ce Sardauna wanda ake laqabi da Gausul Mulki ya yi kira ga Samarin Nijeriya ta Arewa da murya mai qarfi, inda ya ce:

> *A kan quruciyar wannan, Jihar da ta fi kowace girma a Nijeriya, wadda qasa ce mai yawan mutane, kuma ita ce qasar da ta fi kowace girma a Afirka, za ta xauki babban shugabanci lokacin da aka samu mulkin kai ran 1 ga Oktoba na wannan shekarar.*
>
> *Tare da faxaxa ilimin samari da kuma mata na Jihar Arewa, ana alla-alla a sanad da su sosai wannan babbar Jiha, da kuma labarin sauran jihohi na wannan qasar Tarayya, da kuma labarin qasashen "Commonwealth", wadda yanzu qasarsu za ta shiga a ciki.*
>
> *Wannan abu ne musamman da aka keve don sha'anin mulkin kai musamman saboda samarin Jihar Arewa, don lokacin da Jihar ta sami mulkin kanta ran 15 ga Maris bara, Firimiya ya ce, "Muna nufin mu xauki shugabanci wanda ke gaba," kuma ga samarimmu da 'yan matammu, waxanda a shekarun gaba, lallai mu tabbata cewa qasarmu za ta zama abin misali a wajen sha'anin ci gaba, da kyakkyawar manufa, game da al'amura, da kuma 'yanci, ba a Afirka kaxai ba, har ga duniya baki xaya.*[2]

A farkon shagali na cikar shekara da samun mulkin kai, a watan Maris da ya wuce, Firimiya ya sake ba da saqo musamman ga samarin Arewa: "Kun rayu a cikin zamani mai tashin hankali," yaci gaba da cewa,"Qasarmu ta fita daga cikin duhu, ta shiga cikin haske. Kuna tsaye a kan tudu na nasara, don ku sami cikakkiyar dama."

Waxansu kalmomi masu faxakarwa waxanda Alhaji Sir Ahmahu Bello ya faxa a lokacin wannan sha'ani waxanda suka cancanci ambato su ne cewa yanzu

---

[1] *Ibid.*, shafi na 9

[2] *Kai Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na , 1-2

qasarmu za ta shiga cikin qasashen *Commonwealth* kuma ba da daxewa ba za ta shiga cikin Majalisar Xinkin duniya. Wannan ya cancanci a tuna, a cikin wannan lokacin 'yanci, kuma ya ce samun mulkin kai ba shi ne qarshe ba, amma jarabawa ce gare mu duka a lokacin za mu ba da hankalinmu ga aikin qasarmu. Kiran da Sir Ahmadu Bello ya yiwa wa Samari da 'Yanmata sai ya zama babban qulubale ga matasan kowane zamani.[1]

Sir Ahmadu Bello ya ce: "Kai kam ka xan tava tsayawa, ka yi tunani, kuma ka tambayi kanka, me ka yi wa qasarku wanda zai sa ta qara girma, kamar yadda Firimiya ya ce ka yi a cikin watan Maris da ya shige"? Kada kawai ka ce kana xaya daga cikin miliyoyin mutane, ya ce lokacin nan ka ci gaba da tunatar da kowane daga cikinmu, ci gaba, da jin daxin qasa ya danganta a kan kowane mutum, a kan yaqinsu na taimakon kai, da kishin zuci don qaruwar arziqin qasa.

Kirarin Jihar Arewa, shi ne "AIKI DA IBADA" wani abu wanda za a rayu a kai, ka bayar, ka tsare mutane a cikin kowane lokaci. Firimiya ya bayyana ta ta wannan hanya "Duk da tsofaffin al'adunmu, da ci gabammu a cikin sha'anoni zamani, qaramar qasa, ba tare da aiki mai wuya ba, da kuma qoqari wajen aiki, ba za mu yi fatan samun sauran qasashe ba, waxanda ke gaba da mu wajen lafiya, arziqi da kuma jin daxi na mutanensu. Amma aiki sosai shi kansa zai ba mu riba kaxan, sai fa im mun ci gaba da qarfafa addinin da mu ke bi, da xa'a da kuma gaskiya tare da adilci.

Saurayin yau, da kuma nan gaba akwai a cikin zuciyarsa lokacin da ya ce, "Lokaci zai zo, lokacin da ni, da abokan aikina, muka tsufa a wajen aikin qasa, za mu ajiye ragammar gwamnati, kuma na tabbata idan wannan lokaci ya zo, za mu samu daga cikinku (samari) mutanen da za su tafiyar da aikin"[2]

Firimiya kuma ya yi magana a irin qarfafawar da ya samu wajen yin taxi da kowane irin jinsi na jama'a wajen yawan ziyarce-ziyarcen da yake yi a Jiha, wajen biyayya ta mutane iri daban-daban ga gwamnati da kuma qoqarinsu wajen qara arziqi da jin daxi. Kuma ya sake cewa, kowace shekara, tun lokacin da ya zama Firimiya (a cikin sekarar 1954) darajar ci gaban qasa ya qaru amma har yanzu bai haqura ba, cewa ana ci gaba da sauri.

Ingila, da Commonwealth, da Amirka suna taimako, amma Alhaji Sir Ahmadu Bello ya daxe yana tunanin cewa bayanin Nijeriya ga Amirka a iya qara bayyananwa ta hanyar ziyararsa can da waxansu Ministoci. Wannan tunani na halin zama Firimiya ya gan shi lokacin da ya yi rangadi mai nasara tare da Sarkin Kano, da Ministan Ilimi, da Ministan Fidaburdi, da kuma Ministan Qasa da

---

[1] *Kai Da 'Yancin Nijeriya*,

[2] *Ibid*., shafi na , 1-2

Safiyo a Amirka da Canada, wanda ba su daxe da dawowa ba, wanda kuma amfanin da aka samu za a ci gaba da samunsa shekaru masu yawa a nan gaba.

Ta kowace hanya duniyar samari ce, kuma samarin nan masu gaskiya da karsashi za su kyautata, har dai in qasarsu qasa cewadda ba ta daxe da fitowa fili ba, tare da abokai, da shawarwari masu amfani, da taimakon sana'a da kuxi waxanda a ke iya samu tare da abubuwan zamani da aka qago, da irin abubuwan da a ke nema waxanda za su dace da wannan qasa. Har dai waxanda ke jan hankalin samari, wanda shi ne samun damar neman ilimi a qetare – dubban 'yan Nijeriya suna cikin Jami'o'in Ingila – suna kuma qaruwa da sauri, kuma a gida cin samun damar neman ilimi mai zurfi shi aka fi gabatarwa.

Duk da waxannan, a cikin zuciya musamman taubashiyar Sarauniya Gimbiya Alexandra (shekarunta 23) za ta wakilci Sarauniya a wajen shagalin samun mulkin kai na Nijeriya. Mai daraja za ta ji daxin saduwa da ku, in kuma ba haka ba, kai da kanka tabbatacce ne ka kula cewa kana cikin samari miliyan na Nijeriya waxanda su ke sanannu ne na halin zamansu na jin daxi, wanda zai taimake ka sosai a cikin 'yantattar qasa nan gaba.[1]

Da qarfe goma sha-biyu na daren 1 ga Oktoba aka saukar da tutar Ingila, wadda ta yi fiye da shekara sittin tana karkaxawa, sa'an nan a hawar da tutar 'Yantattar Nijeriya. Hawar da tutarmu ita ce alama ta cewa mulki ya komo hannunmu, wato qwaryar da ta je ta dawo. Da sun karva, ga shi mun karvi abinmu.

Yau dai kamar shekara bakwai ke nan maganar ba Nijeriya 'yancinta ya riqa shiga zukatan mutane. Wannan magana ta malalo daga qasashen Kudu ne ta wo Arewa. Ba irin rikice-rikicen muhawarar da ba a yi ba kafin buqata ta biya. Sau tari a kan vata, daga baya a dai-daita.

Ba shakka, komai muka ce na yabon shugabannin jam'iyyoyin siyasa na qasar nan mun rage ne. Aikace-aikacen da suka yi na kiwata Nijeriya a cikin 'yan shekarun nan ba qanqane ba ne, Dole ne mu yaba da wayo, hankali, sanin ya kamata, sanin abin da ke kaiwa yana komowa na shugabaninmu. Don kuwa in ba dominsu ba, da suka haxa kai, suka yaqo wa Nijeriya haqqinta, da har yanzu muna gidan jiya.

Vullowar siyasa a qasar nan shi ne ya kawo mata ci gaba iri-iri. Shi ne kuma ya sa mutanen qasar nan suka qara kishin qasarsu fiye da kima. Kuma sannusannu tare da fahintar juna tsakanin masu mulki (Turawa) da waxanda a ke mulki ('yan Nijeriya), ga shi tsamiya ta juye da mujiya – mulki ya koma hannun 'yan qasa – 'yan Nijeriya. To, a yanzu sai mu ce gari ya waye, safiya ta yi.

To, ba girin-girin ba ta yi mai, kura ta saci ganga. Samun 'yanci wani qasaitaccen nauyi ne ya hau kammu fiye da lokacin da mulki ke hannun Turawa.

---

[1] *Kai Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na 1-2

Mu za mu kaxa zaremmu, mu yi saqa, ba tare da wani ya ce mana wannan saqa ba ta yi kyau ba. Mu za mu qulla, mu za mu warware. Saboda haka, sai mu zage dantse sosai mu yi aiki. Kamata ya yi ma aikace-aikacen da mu ke yi a da mu ruvanya su a yanzu. Kada kuma mu xauki wata hanya dabam wadda ta kaucewa al'adunmu da hanyar zamanmu. Sai dai mu nuna muna iya xaukar wannan nauyi a kafaxunmu. Allah Ya ja zamanin 'yantattar Nijeriya.[1]

Kafin Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello ya tafi Ikko halartar shagulgulan 'yancin Nijeriya, sai da ya yi wa mutanen Jihar Arewa jawabi a rediyo. A cikin jawabin ya ce, mu duka mun san abin da mulkin kai yake nufi. Mu ne za mu gudanar da kowane abu, kuma mu nuna muna iya yin komai. Kowane ya kula da kyakkyawar hanyan nan da aka samu.

Firimiya ya yi gargaxi cewa 'Yanci da Mulkin Kai ba su nufi mu manta da al'adunmu ko hanyar zamanmu da hidimar aikinmu. Ya ce kada a manta wannan Jiha ta fi kowace girma, saboda haka kada a ba da kunya. Kuma a tabbata ba a ta da wani hargitsi ba. Mu nuna hali nagari. Mu yi addu'a a dukkan masallatai da majami'o'i, Allah Ya sa mu wanye lafiya.[2]

Maraba da Gimbiya Alexandra

Yau 1 ga Oktoba da qarfe goma sha-biyu ne dare za a sauke tutar Ingila, a hawar da tutar 'yanci ta Nijeriya mai launin kore da ratsin fari. Lokacin da a ke hawar da tutar 'Yantacciyar Nijeriya, 'yam badujala za su kaxa takenta. Daga nan Nijeriya ta fita daga mulkin wata qasa ke nan xungum, ta kama ragamar mulki.

Ran Jumma'a da Yamma mutanen Ikko za su yi kallon abin da ba su saba gani ba. Wasan Tatu da za a yi a lokacin, mutanen Ikko za su ga zavavvun dawakai da aka hore su sosai guda ashirin da takwas, da kuma 'yan Doka a kansu. Waxannan 'yan Doka za su nuna gwanintarsu ta hawan doki.

A wajen tatu xin nan 'yan badujala iri daban-daban za su yi ta kaxe-kaxe da bushe-bushe. 'yan Sanda za su yi wasa da babur. Zavavvun sojoji xari da ashirin dabiyar za su yi wasannin motsa jiki. Cikin sojojin har da yara arba'in daga Kamfanin Sojan Yara ta Zariya. Har ila yau kuma sojoji za su yi rawar daji. A nan za a yi wasan kwaikwayon yadda a ke yaqi na zamani. Bayan duk an gama waxannan wasanni ne, da qarfe Goma Sha-biyu na dare dai-dai za a saukar da tutar Ingila a hawar da tutar 'Yantattar Nijeriya.

Ran Litinin dai Gimbiya Alexandra wadda ke wakiltar Sarauniya a shagulgulan 'yancin Nijeriya ta sauka Ikko. Cikin waxanda suka tarye ta a filin jirgin saman Ikeja har da Gwamna Janar Sir James Robertson da Firayim Minista Alhaji Sir Abubakar Tafawa Valewa. Bayan ta karvi gaisuwar sojojin Bataliya ta

---

[1] GTK, 30/9/1960 shafi na 3

[2] *Ibid.*

uku sai aka gabatar da ita ga manyan mutane, ciki har da Dr. Nnamdi Azikiwe, wanda aka zava ya zama Gwamna Janar na Nijeriya.

A kan iyakar Ikko da Jihar Yamma, Gimbiya ta sadu da Sarkin Ikko Adele kuma shugaban Majalisar Garin Ikko wanda ya miqa mata jawabin maraba. Cikin amsar da Gimbiyar ta bayar ta ce abin farin ciki ne gare ta da Sarauniya ta naxa ta wakilce ta a cikin wannan lokaci na tarihin Nijeriya. Ta ce a wannan lokaci na tarihin Nijeriya na samun 'yanci wani abin ban sha'awa ne gare ta. Dukkan baqin da aka gayyata daga qasashen duniya sittin sun isa Ikko saboda shagulgulan 'yancin Nijeriya. Amma an ce Afirka ta Kudu ba ta turo wakilinta ba. An ce qila don suna fama da neman ra'ayin mutane da zai sa qasar ta zama Jamhuriya.

Girman Nijeriya ya kai murabba'in mil dubu xari uku da talatin da tara da xari xaya da sittin da tara (339,169), wanda a ciki Jihar Arewa ce ta fi girma, tana da faxin qasa mai murabba'in mil dubu xari biyu da sittin da huxu da xari biyu da tamanin da biyu (264,282). Jihar Yamma faxin murabba'in mil dubu arba'in da biyar da xari uku da saba'in da shida (45,376). Jihar Gabas faxin murabba'in mil dubu ashirin da tara da xari huxu da tamanin da huxu (29,484), sa'an nan Ikko hedkwatar Nijeriya tana da faxin murabba'in mil ashirin da bakwai (27). A tsakiyar shekaran nan dai an qiyasta yawan mutanen Nijeriya ya kai miliyan talatin da bakwai, a ciki mutanen miliyan goma sha-tara da rabi suna zaune a Jihar Arewa ne, miliyan bakwai a Jihar Yamma, miliyan takwas a Jihar Gabas da kuma mutane dubu uku da sittin da huxu (364,000) a Ikko, waxanda ba 'yan Nijeriya ba kuwa sun kai dubu ashirin da bakwai.

A gwamnatin Tarayya dai akwai Majalisar Nijeriya mai wakilai xari uku da goma sha-biyu (312) da Senate mai wakilai arba'in da huxu (44). Tun tuni dai Jihohi ke mulkin kansu. Sun tara da Majalisun Sarakuna da Majalisun Wakilai. A Jihar Arewa a Majalisar Sarakuna tana da wakilai saba'in da shida (76), Majalisar Wakilai xari da talatin da shida (136), A Jihar Yamma aqwai ta da Majalisar Wakilai tamanin (80) Majalisar Sarakuna hamsin da biyu (52). A Jihar Gabas: Majalisar Sarakuna sittin da uku (63), Majalisar Wakilai tamanin da huxu (84).[1]

Nijeriya ta samu 'yanci sai ta samu takenta na farko kamar haka:

Nijeriya mun gaishe ki,
Qaunatacciyar qasa,
Harshe qabila sun rabu,
Mun zama 'yan'uwa,
Da alfarma mu bauta wa,
Qasarmu Nijeriya.

[1] GTK, 30/9/1960 shafi na 3

Tutarmu alama ce,
Gaskiya da adalci,
Cikin lumana ko yaqi,
Ita ce ribarmu,
Da za mu bar wa 'ya'yammu,
Abin alfahari.

Allahn dukkan halitta,
Ji wannan roqommu,
Taimake mu gina qasa,
Inda ba danniya,
Cikin lumana da yalwa,
Ta-sami albarka.[1]

Bayan wata tara da ziyarar Wazirin Ingila ga Nijeriya sai Nijeriya ta qara samun Babbar Baquwa wato Mai Daraja Gimbiya Alexandra Ta Kent. Wadda ita ce ta wakilci Mai martaba Sarauniya a bukukuwan 'yanci. A wannan lokaci sai aka shirya ziyararta Arewa daga 11 zuwa 15 ga Oktoban shekarar 1960. A wannan lokaci ne kuma Mai girma Firimiyan Arewa ya yi lale da marhabin da wannan Babbar Baquwa.

Princess Alexandra Helen Elizabeth Olga Christabet wadda za ta wakilci Sarauniya a Bukin Samun 'yancin Nijeriya, za ta sauka Bida da Makurxi ran 11 ga watan Oktoba, za ta wuce zuwa Kaduna a wannan rana, Ran 17 Gimbiya za ta tashi a jirgin sama zuwa Maiduguri. Washegari Gimbiya zata wuce zuwa Kano daga nan za ta shiga jirgin sama zuwa London da maraice.[2]

Ita wannan Babbar Baquwa kwana biyar tayi a Arewa, a wannan lokaci ta ga muhimman abubuwa na Jihar, mutanenta da ayyukansu. A ziyararta Kaduna ta sadu da Wakilai a lokacin da suke taronsu a *Lugard Hall*. Daga Kaduna sai aka shirya ta kai ziyara fadar Sarkin Zazzau da Shehun Barno a Maiduguri a lokacin da ta ziyarci waxannan garuruwa, daga qarshe sai ta kai ziyara birnin Kano.[3] Gimbiya Alexandra makusanciyar aminiyar Sarauniya ce, abokin wasanta na farko a wurin marigayi tsohonta, makusancin taubashinta na farko wurin uwa kuma shi ne Duke of Edinburgh.[4] Shi ne qasaitaccen baqon Arewa a lokacin shagalin samun Mulkin kai, a watan Maris na shekarar 1959.

---

1 GTK, 30/9/1960 shafi na 3

2 *Ku Da 'Yancin Nijeriya*, shafi na 5

3 *Ibid*.

4 *Ibid*. shafi na 6

Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato ya ce a wannan shekara ta 'yanci yana roqon kowane xan Nijeriya ya sa wannan babbar niyya a zuciyarsa, "Haxa kai a cikin Jiharsa, haxa kai a cikin qasar Tarayya, haka kuma haxa kai cikin qasashen Commonwealth." Wannan na cikin jawabin maraba da Firimiya ya yi wa Gimbiya Alexandra a haxaxxen taron Sarakuna da Wakilai a *Lugard Hall*.

Kuma Firimiya ya ce sun tabbata gaba ba za ta yi kyau ba gare su a Nijeriya sai in Tarayya ta zama al'umma guda haxaxxiya, wadda ke da xa'a ga mutanenta, ta kuma yi xa'a ga buqace-buqacen da suka shafe su baki xaya, kuma ba da kula da bambancin addini ba, ko kuma bambancin Jiha. Ya ce, "Mu mun yi matuqar niyya don manufarmu ta zamo samun haxa kai da kuma girmama ra'ayoyin sauran jama'a."

Tun farko sai da Firimiya ya ce mutanen Jihar nan sun yi xauki don jiran isowar Gimbiya. Ya ce yadda Mai Alfarma Sarauniya ke kula da sha'anunuwammu ko da yaushe lallai ba biyayya wadda take wajibi gare mu kaxai ta cancanta ba, a'a, har da matuqar qauna wadda ta yaxu ga Fadar Sarauniya a cikin 'yan shekarun nan cikin zukatan mutanen qasar nan, manya da qanana. Ya ce yana roqon Mai Daraja ta isar da godiyar xa'a ta mutanen Jihar nan zuwa ga Mai Alfarma Sarauniya.

Firimiya ya ci gaba da cewa, "Kowace ziyara ta xan gidan sarauta ko yaushe ta kan qara mana qarfi, amma ke naki zuwan a cikinmu abu ne wanda ya shafi kowa. Abu ne na kulawa ga samarinmu." Ya ce a wannan sashe na qasar Tarayya akwai abubuwan damuwa game da girman qasa da kuma bambanci. Amma an yi nisa wajen kushe su, saboda bin hanya guda kurum, ita ce ba da gaskiya ga son haxa kai. Firimiya ya ce bayan qasar Tarayya ana duban haxuwar qasashen Commonwealth ta zamo turken haxa kai a duniyan nan ta yau, wadda hankalinta ba kwance yake ba.

A qarshe dai Firimiya ya ce, "Mu a wannan Jiha mun xauki al'adunmu da girma qwarai don su kawo mana jama'a amintattu da kuma mulki maras rikici. Muna kuwa da niyyar mu yi iyakar ikonmu mu tsare abubuwan da ke da amfani a cikin hanyar zamanmu na duniya. Amma mu ba mu da nufin dukkan al'adu tsarkaka ne, dole su tabbata mun san wajibi ne mu lura da canje-canjen zamani. Ba za mu yarda jama'armu ta zama kafe ba, ba motsi, domin in mu ba mu samu abu ba wanda za mu iya, mu miqa wa na baya, to, ba mu cancanci mu karvi abin da muka gada ba." Ya yi mata fatan jin daxin zama cikin Jihar nan, da komawa gida lafiya.

A cikin jawabin Sarauniya wanda Gimbiya Alexandra ta karanta, jawabin ya bayyana irin muhimmin harkokin da ke gaban Jihar Arewa kafin ta samu Mulkin Kanta. Jawabin ya kuma nuna nasarar Jihar da har ta yi qoqarin kawar da waxansu matsaloli da ke gabanta, ta kuma yarda da karvar 'yancin Nijeriya.

Wannan duk ya faru ne cikin shekaru qanqane. Jawabin ya ce yana fata Jihar Arewa za ta yi iyakacin qoqarinta na haxa kai don samun nasarar 'yancin Nijeriya. Ta ce, "Na amince ba Nijeriya kaxai za ku taimaka ba, har ma za ku yi wani babban taimako ga duniya."

A qarshen wannan jawabi, sai Gimbiya Alexandra ta yi nata jawabin. Ta ce, ta gode wa Firimiya kan irin jawabin da ya yi game da ita. Ta shaida masa cewa ta sha jin labarin Jihar Arewa tun tana Ingila, amma irin abubuwan da ta gani ya fi yadda aka shaida mata. Gimbiya ta ce, bisa duka babban nauyin da ke kafaxunku mutanen suna aiki matuqa, kuma suna zaman jin daxi.

Na ji labarin waxansu ziyarce-ziyarce da zan yi a Jihar, ina alfahari da in shaida muku cewa na samu labarin shaharar mutanen Jihar Arewa – mutane ne masu iya shugabanci." A qarshe ta yaba wa Firimiya kan yadda ya xaukaka Jihar Arewa har aka santa a sauran qasashe. Daga nan ta miqa masa kofen na Shirin Tsarin Mulkin Nijeriya da Jihohinta.

Gimbiya Alexandra dai ta fara rangadin Jihar Arewa daga ziyarar Bida daga Enugu. A nan gwamnan Jihar Arewa da Firimiya suka tarye ta, sa'an nan Firimiya ya sadad da ita ga Etsu Nupe da sauran Sarakunan lardin Neja. A nan ta karvi furanni daga hannun wata yarinya. Daga nan ta shiga mota zuwa fadar Etsu nisan mil uku, amma a kan hanya mutane dubbai waxansu kan dawakai da 'yam makaranta dubu biyu sun jeru don yi mata maraba. A fada, ta sadu da Etsu cikin Majalisa inda ta ba shi wani qunshi amma ba a san abin da ke ciki ba.

Lokacin da take rangadin sana'o'in hannu na Bida ta yi sha'awar duwatsun wuya har ma ta sayi waxansu. A cikin gidan Etsu kuma ta sadu da matansa huxu da sauran iyalansa. A nan ne aka ba ta kyautar qyallaye huxu masu launi daban-daban don nuna irin tufan Nufawa. Kafin dai ta shiga jirgin sama zuwa Kaduna sai da aka nuna mata wata yarjejeniya da aka sa hannu tsakanin Turawan Kamfani wato *Royal Niger Company* da Etsu Nupe na lokacin cikin shekarar 1887.

A Kaduna ma an yi mata kyakkyawar maraba. gwamnan Jihar Arewa da uwargidansa tare da Firimiya suka taryeta da ta sauka a jirgin sama. A nan Kuma Firimiya ya sada ta da Sarkin Kano Alhaji Sir Muhammadu Sanusi; Muqaddashin Cifjojin Arewa Mr. Smith; Babban Alqalin Arewa Sir Shehu Awad; Shugaban Majalisar Sarakuna; Sarkin Gwandu; Shugaban Majalisar Wakilai Alhaji Umaru Gwandu; Sarkin Katsina da sauran Ministoci.

Daga nan ta nufi masaukinta a gidan Gwamna, tana tafe tana amsa gaisuwa daga dubban mutane da suka yi dafifi a hanya suna yi mata maraba. A ran nan kuma da dare Babbar Baquwa ta kai ziyara hedkwatar Daular Usumaniyya a inda dawakai dubu uku suka yi wa Gimbiya hawan Dabar a Sakkwato. Wannan yana cikin gudunmawar Arewa game da shagulgulan 'Yanci, Garuruwan da suka shiga Dabar xin su ne Yawuri, Argungu da Gwandu. Har ila yau kuma ran Asabar, aka

yi wani qasaitaccen hawan Daba a Maiduguri dominta.[1] Saboda haka ta ce abubuwan mamakin da ta gani sun fi labarin data ji a kan shaharar mutanen Arewa.

Mai masaukin wannan Babbar Baquwa, Firimiyan Jihar Arewa ne ya yi maraba da zuwanta Jihar Arewa. Ya kira qasaitacciyar liyafa a sabon gidansa. Firimiyan ya yi jawabin maraba ga Mai Daraja Gimbiya Alexandra a Gidan Shawara, a ranar 12 ga Oktoban shekarar 1960. Ga jawabinsa:

Bismil Lahi Arrahamani Arraheem:

Ya Mai Daraja, mutanen Jihar nan sun yi xauki don jiran isowarki nan. Na fara da godiya ga Maxaukakin Sarki da ya baki ikon zuwa gare mu lafiya qalau. A cikin 'yan shekarun nan mun sha sauraren shawarori kyawawa da kuma kalmomi waxanda ke qara mana qarfi daga iyalin Fadar Sarauniya. Zan iya cewa, da qasqantad da kai, aikin da muka yi har zuwa yau ya nuna mun yi aiki na gari da shawarwari da muka samu daga Fadar. Kuma sai in ce yadda Mai Alfarma Sarauniya take kula da sha'anoninmu ko da yaushe lallai ba biyayya, wadda take wajibi gare mu kaxai ya cancanta ba, a'a, har da matuqar qauna wadda ta yaxu ga Fadar Sarauniya a cikin 'yan shekarun nan cikin zukatan mutanen Qasar nan, manya da qanana. Al'amarin da mu ke ciki yau da kuma zaman ki da mu qarin shaida ne na hankalinta da kuma sanin ya kamata, a kan matsayinta na Shugabar Qasashenta. Allah Ya tsawaita shugabancinta a kan wannan taron qasashe waxanda suka zama jagora ga sauran duniya wajen tabattadda zaman lafiya da 'yanci na gaskiya. Muna roqon ki Mai Daraja ki yarda ki isar da godiyar xa'a ta mutanen Jihar nan zuwa ga Mai Alfarma Sarauniya.

Ke kuma Mai Daraja lokacin da ni ke isar da maraba da fatar alheri ta mutane na zuwa gare ki, ina fata ba wuce wuri ba ne gare ni in na ce ba za a iya zavo fiye da ke ba don wakiltar Sarauniya a wannan shekara ta 'yancinmu. Na tabbata za ki yi ayyukanki na sarauta da natsuwa wadda ta dace da matsayinki, sa'an nan da bajinta wadda ta dace da quruciyarki. Kowace ziyara ta xan Gidan Sarauta ko yaushe ta kan qara mana qarfi, amma ke na ki zuwan a cikinmu abu ne wanda ya shafi kowa. Abu ne na kulawa ga samarinmu. Qaramcin shekarunki da kula da al'amuran yau, wanda ke gare ki, da fitowa daga gidan Sarauta wanda yana cikin gidaje mafi xaxewa da kuma samun girmamawa a duniya, abubuwa ne

[1] GTK 14/10/1960, shafi na .11-12

waxanda za su qayatar da mutane waxanda su ke qoqari su dasa dabarun zamani a kan al'adun da suka gada. Abin da ki ke faxa da kuma misalan da ki ke nunawa za su faxakad da mutanenmu, tsofaffi da yara, su sa su yi iyakar qoqarinsu.

Yanzu dai Mai Daraja kin yi tafiya mai yawa har yadda za ki iya ganin ximbin girman qasarmu da kuma bambancin da ke cikinta. A wannan sashen ma na Qasar Tarayya muna da abubuwan damuwa gameda girman qasa da kuma bambanci. Amma mun yi nisa wajen kaushe su saboda bin hanya guda kurum, ita ce ba da gaskiyarmu ga son haxa kai. Yanzu kuma wannan hanya ita mu ke bi da gaske da kuma himma game da sha'annuwanmu da sauran 'yan Nijeriya, ko'ina suka fito. Mun tabbata gaba ba zata yi kyau ba gare mu a Nijeriya sai in Tarayya ta zama al'umma guda haxaxxiya, wadda ke da xa'a ga mutanenta ta kuma yi xa'a ga buqace buqacen da suka shafe su baki xaya, kuma ba da kula da bambancin addini ba ko kuma bambancin Jiha. Mu mun yi matuqar niyya don manufar mu ta zamo samun haxa kai da kuma girmama ra'ayoyin sauran jama'a. Za mu kuma yi iyakar zarafinmu mu ga an kai ga wannan manufa ba tare da vacin rai ba. Bayan qasarmu ta Tarayya kuma muna duban haxuwar qasashen Commonwealth ta zamo mana turken haxa kai a duniyan nan ta yau wadda hankalinta ba kwance yake ba. Mun sani a cikin duniya ta yau wadda ba amincewa a cikinta, qasashen "Commonwealth" kamar tsibirin hankali ne in da komi tsananin bambanci ana iya shawara game da shi ba tare da zage-zage ba, ko kyacewa. Daga wannan shekara ta 'yancin ina roqon kowane xan Nijeriya ya sa wannan babbar niyya a zuciyarsa, "Haxa Kai a cikin Jiharsa, Haxa kai a cikin Qasar Tarayya, haka kuma Haxa Kai a cikin qasashen Commonwealth.

Ya Mai Daraja, mu a wannan Jiha mun xauki al'adunmu da girma qwarai don su suka kawo mana jama'a amintattu da kuma mulki maras rikici. Muna kuwa da niyyar mu yi iyakar ikonmu mu tsare abubuwan da ke da amfani a cikin hanyar zamanmu na duniya. Amma mu ba mu nufin dukkan al'adu tsarkaka ne, dole su tabbata, mun san wajibi ne mu lura da canje canjen zamani. Ba za mu yarda jama'ammu ta zama kafe ba, ba motsi, domin in mu ba mu samu wani abu ba wanda za mu iya mu miqa wa na baya, to ba mu cancanci mu karvi abin da muka gada ba.

Mai Daraja, dukammu muna yi maki godiya, muna fata ki ji daxin zama cikin Jihar nan, ki kuma koma gida lafiya." [1]

A ranar Asabar 8 ga Oktoban shekarar 1960 aka yi qasaitaccen shagali a gidan gwamnan Jihar Arewa Sir Gawain Bell don liqawa waxansu manyan mutane lambobin da Sarauniyar Ingila ta ba su. Firimiyan Jihar Arewa Alhaji Sir Ahmadu Bello, 'yan Majalisar Wakilai ta Jihar Arewa da waxansu manyan ma'aikatan gwamnati suna daga cikin waxanda suka halarci kallon bikin.

An liqa wa Alhaji Umaru Gwandu da M. Aliyu Mustafa, Lamixon Adamawa lambar O.B.E. Miss Elizabeth Theodora Mess ta samu lambar O.B.E don qwazonta kan inganta harkokin asibitin Mishan. M. Abdullahi da Alhaji Muhammadu Wazirin Adamawa sun samu lambar M.B.E. Haka kuma am ba Miss Ruth Earl Utz lambar M.B.E. ta girmamawa. M. Umaru Birnin Kabi da Alhaji Idi Musa sun sami lambar B.E.M. (ta farar hula).[2]

Mai martaba Sarauniyar Ingila cikin lambobin Sabuwar Shekara da take bayarwa, ta yi farin cikin ba da waxannan lambobin K.B.E.: ga (wato sun zama Sir) Shehun Barno, Alhaji Umar Ibn Mohammed El-Kanemi, C.M.G., C.B.E. xan shekara 89 da Shehu Awad Mohammed Ahmed, Babban Alqalin Jihar Arewa.

Lambar C.M.G.: Mr. Bruce Greatbatch, C.B.O., M.B.E., Babban Sakataren Firimiya da Sarkin Gwandu Alhaji Haruna C.B.E.

Lambar C.B.E.: Mr. M. J. Bennion M.B.E., Shugaban Makarantar Koyon Aikin Mulki.

Lambar O.B.E.: Malam Yahaya Gusau, Babban Sakataren Ofishin Ministan Al'amuran Qasa na Jihar Arewa; Malam Abba Habib, Wazirin Dikwa; Alhaji Muhammadu Sani Yola, Sarkin Shanu, Kano; Mr. S.S. Richardson, Kwamishinan Kotunan 'Yan Qasa a Jihar Arewa; Mr. A.G. Waterman Branch, Babban Likita a Asibitin Jos da Mr. E.C. Gilles, Shugaban Makarantar Koyon Aikin Asibiti a Kano.

Lambar M.B.E.: Malam Audu Gusau, Injiniyan En'e ta Sakkwato; Alhaji Ahmadu Rufa'i Daura, xam Majalisar En'en Kano mai kula da ilimi; Alhaji Isa Shittu Dutse, Qaramin Sakataren Firimiya; Pastor David Lot, xam Majalisar Wakilai ta Arewa; Mr. D.H. Robertson, manajan Aiki a ofishin *Ministan Fidaburdi* da Miss Annie Paterson Dick, Matron.

---

[1] AH/GP/SA/A34

[2] GTK 14/10/1960

Lambar B.E.M.: Malam Dapci Damboa mai aiki a asibitin kula da kutare a lardin Barno (S.U.M.) da Mr. John Michael Onyia, Babban Nas a asibitin Maiduguri.[1]

A qarshen ziyararta Arewa sai Babbar Baquwa ta nuna godiya da farin ciki ga jama'ar wannan jiha wadda ta yi alfahari da ziyartarta.

Gimbiya ta Gode wa 'Yan Arewa

Wannan babbar Baquwa ta samu kyaututtuka masu yawa waxanda kuma suka faranta mata rai qwarai da gaske. Kyautukan da aka bai wa Gimbiya Alexandra ta Kent a lokacin ziyararta ta Jihar Arewa ta Nijeriya am faxi sun kasance kamar haka:

Kyautar gwamnati: Waxansu kyawawan tintin, jakar yin sayayya ta mara da jakunan riqewa a hannu tare da qwayayen jimina.

Kyautar Sardauna: Fatun damisa guda biyu, mataccen qaramin kada da aka cika shi, alkyabba guda, mafici na gashin jimina da na gashin tsuntsun Makka.

Kyautar 'Yarsa Nana: Ta bai wa Gimbiya zoben azurfa, warwaron hannu, xan kunne da takalmi faxe na Sakkwato a makwafin matan Firimiya. Gimbiya ta sanya waxansu daga cikin abubuwan nan da aka ba ta kyauta a lokacin da take Maiduguri, kuma ta sanya waxansu a lokacin da ta shiga jirgin sama zuwa gida Ingila. Firimiyan Jihar Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello, ya gode wa matanen Jihar Arewa saboda kyakkyawan halin da suka nuna a lokacin da aka yi shagalin samun 'yancin. Cikin wata sanarwa da ya bayar a Kano, Alhaji Sir Ahmadu Bello ya tuna da gargaxin da ya yi game da wannan kafin ya tashi zuwa Ikko don halartar sashe na farko na shagalin. Ya ce,"ina matuqar farin ciki, cewa mutanen Jihar Arewa sun ji wannan gargaxi, kuma sun nuna kyakkyawan halin da nake buqata.

Firimiya kuma ya ce yanzu shagulgulan sun qare, yana kuma da wani abin da zai ce. Sabon gargaxin da Firimiya ya yi, ya roqi kowa da kowa ya yi aiki mai tsanani fiye da da don tabbatar da 'yancin nan da aka samu.

"Kowane xaya daga cikinmu", in ji Alhaji Sir Ahmadu Bello,"ko mene ne a ke kiransa, yana da aikin da zai yi na biyayya ga Jiharsa da sunan Nijeriya.[2]

A qarshen rangadinta na Jihar Arewa, wanda kuma shi ne Jihar Arewa ta aika da gaisuwar ladabi na mutanen Jihar Arewa ga Gimbiya Alexandra ta Kent kafin ta bar Kano a qarshen ziyararta zuwa Ingila.

---

[1] *Ibid*., Ta 988 6/1/1960

[2] GTK, Ta 977 21/10/1960

Cikin saqon gwamnati data aiko Babbar Bakuwar ta ce kwana biyar da Gimbiya ta yi a Jihar Aewa, mutane sun yi matuqar farin ciki. Ta qara da cewa, "Irin sha'awarki da kika nuna a dukkan abubuwan da kika gani, abin farin ciki ne."

Cikin amsa jawabin, Gimbiya Alexandra ta godewa dukkan mutanen qasar Tarayya ta Nijeriya saboda kyakkyawar maraba da kyakkyawar xawainiyar da suka yi mata a ko'ina, wanda ta bayyana zaman farin ciki ne da ba za ta manta da shi ba. Ta ce ta yi matuqar farin ciki game da irin kyakkyawar karvar da mutane suka yi mata a ko'ina ta tafi.

Gimbiya ta ci gaba da cewa, 'Ko yaushe zan tuna da halin abokantaka bisa ga irin yadda jama'a su ke gaishe ni ko'ina na ratsa cikin qasar." Ta bayyana alfaharinta bisa shaquwa da Nijeriya a wannan muhimmin lokaci na tarihinta, kuma ta yi farin cikin samun damar halartar shagulgulan samun 'yanci da qasar ta yi.

Ta qare da cewa, "Ina fata yadda kuka fara da kyau, ku ci gaba cikin farin ciki, zaman lafiya da qaruwar arziqi." Da farko kuwa, lokacin da Gimbiya ta isa Kano daga Maiduguri, sai da ta sami kyakkyawar maraba daga matanen Kano. Mutane dubbai, waxansu bisa dawaki su ne suka rufa mata baya a lokacin da ta shiga mota zuwa fadar Sarkin Kano. A cikin motar, wadda take buxaxxiya ce, suna tare da Firimiyan Jihar Arewa ne, Alhaji Sir Ahmadu Bello. [1]

To, komai ya yi farko zai yi qarshe. Mulkin Mallaka ya kawo qarshe. Tarayyar Nijeriya ta sami 'yanci kuma ta shiga qasashen da ke aminci da Ingila. Haka zalika mulki ta kan Sarakuna ya yi ajali. Jihar Arewa kuma ta koma qarqashin mulkin 'ya 'yanta gaba-gaxi sai ta shiga wani sabon falle na tarihi. Amma kuma mulki ta kan Sarakuna ya tafi ya bar baya da qura. Saboda haka ne Gwamna Lugga wanda ya garqama wa Arewa irin wannan mulkin ya haxu da fushi Alhaji Dr. Abubakar Imam. A wannan lokaci ne ya kamata a tuna arangamar da Dr. Imam ya yi da Gwamna Lugga. Domin yanzu ne ya kamata a fahimci illolin *Indirect Rule* a Arewa, da kuma yadda za a yi maganinsu.

Fushin Abubakar Imam

Mulki a fakaice ya kan Sarakunan Arewa wato *Indirect Rule* abu ne da ya zama wajibi ga Turawan Mulki su aiwatar. Saboda rashin isassun jami'ai da kayan aiki. Arewa tana da girman qasa mai faxin gaske wadda aka qiyasta a shekarar 1900 ya kai mil dubu xari uku da ashirin (320,000 miles). Har-ila-yau yawan jama'arta ya kai miliyan goma sha-xaya a farkon shigowar Turawa. gwamnatin mulki kuma nada qarancin ma'aikata ainun.

---

[1] GTK, Ta 977 21/10/1960

An qiyasta cewa a shekarar 1900, idan za a karkasa jami'an mulki ga yawan jama'a, to, ya ya jami'ai guda tara za su mulki jama'ar da ke da yawan miliyan goma sha-xaya, a kuma qasa mai faxin gaske? Wato kowanne jami'in mulki zai sami yawan jama'a da suka kai yawan miliyan xaya ko biyu ke nan. A wannan lokaci kuma ga rashin qudi da gwamnati ke fama da shi. Saboda waxannan dalilai sai Ingila ta zavi mulkin Arewa takan Sarakunansu, wanda Gwamna Lugga ya aiwatar. An xauki wannan samfurin mulki ne saboda akwai tsarin shugabanci mai kyau a Arewa, wanda Sarakuna ke aiwatar wa.

Ba da 'yancin Kai a Nijeriya, an yi shi ne kamar yadda aka mallaki Nijeriya wato ta yanki-yanki. Jihohin Yamma da Gabas sun sami mulkin kansu ne a shekarar 1957. Bayan shekara biyu sai Arewa ta samu nata.

A watan Maris xin shekarar 1959, Arewa ta samu Mulkin kai, Nijeriya kuma ta samu 'Yancin kai a watan Oktoba na shekarar 1960. Mulkin *Indirect Rule* a Arewa sai ya yi ajali, ya zo qarshe. Komai ya yi farko zai yi qarshe. Mulkin *Indirect Rule*, ya zo ya tafi. Amma ya bar Arewa da illoli masu munin gaske. A lokacin da ake aiwatar da wannan mulki, Turawa sun sami damar raba kan shugabannin Arewa saboda sun haddasa gaba tsakanin sashe daban-daban na jama'a. A lokuta da dama sai suka riqa lavewa da guzuma suna harbin karsana a salon mulkinsu na *divide et impera*. To, lokaci ya zo qarshe Turawan Mulki sun koma gida, amma sun bar Arewa na artabu da illolin *Indirect Rule*. Alhaji (Dr) Abubakar Imam ya bayyana fushinsa ga waxannan illoli ga shugabannin da suka haddasa su.

Idan akwai wanda ya fahimci *Indirect Rule* da kuma illolin da suka haddasa wa Arewa, ba kamar mashahurin mutumin nan Alhaji Dr. Abubakar Imam. Wannan irin mulki da Turawa suka yi wa Arewa, sai ya zama wani babban dabaibayin hana ta ci gaba. Dr. Abubakar Imam ne kawai ya fito fili, ya yi tir da *Indirect Rule*, ya kuma fasa dami a kan kaba. Amma kafin mu ji yadda Gwamna Lugga ya haxu da fushin wannan gwarzo kuma barde mai kishin Arewa, sai mu ji abin da Sir Bryan ya ce game da Imam, kamar haka:

> *A wannan lokaci ne kuma Allah Ya kawo wa Arewa wani xa, yaro, wanda a ke kira Abubakar Imam, wanda tunaninsa, da halinsa suka sami karvuwa ga kusan dukkan samari 'yan'uwansa, masu tasowa a Arewa, ba mai iya gane iyakacinsa saboda rubuce-rubunsa a cikin harshen Hausa yake yi. Saboda haka mutanen Ingila da basu iya karanta rubuce-rubucensa, ba su san abin da ke dafuwa ba. Haka ma mutanen Lagos suka zauna cikin jahilcinsa. Amma abin da ra'ayin nan nasa ya haifa ba qaramin tasiri ya yi ba a cikin jagorancin tunanin mutanen Nijeriya ta Arewa.*

Abubakar Imam a sa'an nan yana da kamar shekaru 35. An haife shi a cikin wata zuriya mai mutunci. A Katsina Kwaleji ya gama makaranta, a nan ya ci takarda ya zama Malamin Turanci. Ya zama shi ne xaya daga cikin waxanda suka tava talifin littattafai a cikin harshen Hausa.

Ya wallafi littattafai da dama saboda Makarantun Elemantare a Arewa. Saboda haka sa'ad da gwamnati ta yi shawarwari yin Jarida ta Hausa, bata sha wata wahala ba ga binciken wanda zai fara zama Edita na ta. Duk idanduna suna ga Abubakar Imam. Shi ma ne ya sanya wa Jaridar suna"Gaskiya Ta Fi Kwabo [1].

Dr. Abubakar Imam shi ne Sadaukin da ya yiwa wani Sadauki karen tsaye. Don Allah Ya yi shi mutumne kuma xan Arewa na asali, wanda ya yi ficewajen faxin gaskiya komai xacinta. A taron Edita da Edita da aka yi a Ingila ne Lugga ya haxu da fushin Imam.

Ran Lahadi, 15 ga Agustan shekarar 1943 Mai Daraja Lord Lugard ya gaiya ci wasu Editocin Yammacin Afirka zuwa gidansa da ke kusa da Dorking. Editoci huxu ne suka amsa wannan gaiyatar; Mista Ofel daga qasar Gwalkwas (Ghana), da Mista Thomas daga qasar Gambiya, da kuma Mista Thomas da Alhaji Abubakar Imam daga Nijeriya.[2] Su waxannan Editoci sun tafi taron Edita da Edita na Afrika ta Yamma ne da aka yi a Ingila. Xaya daga cikin waxanda aka zava tare da Alhaji Abubakar Imam, shi ne Dr. Nnamdi Azikiwe, wanda shi ne Edita na Jaridar West African Pilot a lokacin nan.[3]

Da suka tafi Ingila, sau biyu Gwamna Lugga, Lord Lugard, yana kiran shi Alhaji Abubakar Imam domin su yi shawara.[4] A wannan saduwar cewannan gwarzo ya fexe biri har wutsiya, ya gaya masa illolin da samfurin mulki na *Indirect Rule* wanda shi Gwamna Lugga ya kafa, suka haifar a Arewa. A wannan lokaci ne Abubakar Imam ya fito fili ba tare da tsoron komai ba ya faxi gaskiya. Don kuwa, shi ne ya qirqiro da taken "In zaka faxi, faxi gaskiya, komai taka ja maka ka biya!" A wannan lokaci, a kuma gaban mashahurin Baturen da ya yi suna a duniya, Alhaji Abubakar Imam ya nuna masa a zahiri, "Gaskiya Ta Fi Kwabo!" Domin ya bayyana masa illolin da samfurin mulkinsa ya haifa a Arewa.

A wannan haxuwar tasu da Gwamna Lugga ya nuna hikima da zalaqa da qwarewa wajen nuna fahimtar luggar Turanci. Ba tare da vata lokaci ba ya cewa

---

1 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na . 30-31

2 *Ibid*. shafi na 77

3 *Ibid*., shafi na 31

4 *Ibid*.

tsohon Gwamna: "Mulkin *Indirect Rule* ya kasa tafiya tare da sauyawar zamani." Wato ya zama tarnaqin hana Arewa ci gaba. Ya ce: "Ga tsari mai kyau in mutun ya karanta a takarda, amma abin da Turawan Mulki waxanda ake aikawa da su, don tafiyar da shi a Nijeriya ta Arewa ke yi bai zama abin yabo ba. Qin kulan Turawan ya sanya tsarin ya zama abin zargi, abin suka, da abin tsattsaga"[1] Shi ma Sir Bryan ya bayyana wannan arangama da Dr. Imam ya yi da Lord Lugard, ya ce: "Abubakar Imam ya shiga sukar Turawan Mulki kaca kaca a gaban Gwamna Lugga. Ga Xan Hausa, Sir Hanns Vischer tare da su."[2]

Ko kaxan shugabannin Jam'iyyan Mutanen Kudu ba su so *Indirect Rule* ba, sai suka xana masa karan tsana! Iliminsu da gogewarsu da huldarsu da Turawa, sun nuna masu cewa wannan samfurin Mulki ba zai haifar da xa mai ido ba. Sir Bryan, ya yi nuni da haka, inda ya ce:

> *Waxannan shugabanni na waxannan jam'iyyoyi, suna da manyan abokan gaba biyu a cikin tsarin mulkin Nijeriya. Babban abokin gabansu shi ne, irin samfurin mulkin Gwamna Lugga, Indirect Rule da kuma Shari'o'in musulunci da Shari'o'in al'ada. Hasali dai duk hanyar shari'a wadda ta sava wa irin ta Ingila ba su qaunarta. Irin samfurin mulkin da ake kira Indirect Rule da Turanci shi ne muka gaya muku a baya. Shi ne a mallaki qasa ta hannun masu mulkinta na gargajiya, ba a ture su gefe guda ba. Mutanen Ikko, sun koyi irin dabarun zaman duniya irin na Ingilishi, saboda haka suka qi wannan samfuri da zai sa a mallake su ta hannun Sarakuna. Suka ce irin wannan samfurin mulki, ya sanya Sarakunansu sun zama kakaki, ba su da aiki sai busa Odojin mulki irin wanda Turawa su ke so. A wannan ra'ayi, nan babban bambanci ya zo tsakanin qasashen Nijeriya ta Kudu da Nijeriya ta Arewa. Arewa suna ja zuwa Gabas, Kudu suna ja zuwa Yamma. Su Arewa a sa'an nan, ba su fara sanya qafa suna shurin irin samfurin suna mulkin gargajiya ba, wanda mulkin Turawa ya same su a kai. Ko da shike yadda a ke tafiyar da mulkin ya fara samun shuri har da tokari.*[3]

Sir Bryan ya yi tsokaci a kan abubuwan da Dr. Imam ya faxa. 'ya ce: "Da yawa cikin soke-soke da ya yi mana, ya rubuta, ya aika wa Gwamna Lugga da su a rubuce har Ingila. Ban da su ma ya rubuta waxansu soke-soken namu a cikin

---

1 *Ibid.*

2 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 31

3 *Ibid.*

Gaskiya Ta Fi Kwabo a jerinsa na Edita.[1] Samfurin mulkin *Indirect Rule* ya riga ya yiwa Arewa mummunan varna, ya raunana da munana mulkin Sarakuna. Don a akasarin lokaci, ya maida su kakakin Turawan mulki, ko suna so ko basa so, a wajen zartar da Mulkin Mallaka a Arewa. Wannan samfurin mulki ne ya haddasa gaba da adawa a tsakanin Sarakuna da 'yan Siyasa, ya kuma zama wani babban tarnaqin ci gaban Arewa baki xaya. Domin ba a aiwatar da Mulkin Mallaka don ya kawo ci gaban qasa, ba sai dai ya maida ita fifa-iya koma baya, jama'arta kuma qyale qyale huhun ma'ahu. Domin haka ne Turawan suka yi amfani da tsarin mulkin, suka lave da guzuma don su harbi karsana. Maganin illolin da *Indirect Rule* ya haddasawa Arewa su ne qalubalen da ke gaban shugabanni da jama'ar Arewa a yanzu don samun kaiwa ga ci gaba.

A ran Talata, 17 ga Agustan shekarar 1943, gwamnan Lugga ya gaiyaci Dr. Abubakar Imam zuwa gidansa don su kaxaice su tattauna batun *Indirect Rule*. Sir Hanns Vischer, wanda aka fi sani da XanHausa ne ya raka shi. A wannan lokaci ne mashahurin Editan Gaskiya Ta Fi Kwabo, ya samu walawa sosai ya kuma fasa dami kan kaba ya ce: "Ko da yake a matsayina na Edita ban sami wasiqa da ke sukar tsarin Indirect Rule a Arewa ba, amma kuma ta ciki na ciki. Domin akwai abu guda da ke damun mutane musamman ilimi wanda shi ke damuna. Mutane sun yi qorafin cewa duniya na canzawa amma Indirect Rule ya yiwa Arewa tarnaqi ya hanata ci gaba."[2]

A wannan lokaci sai Lugga ya nemi qarin bayani wataqila ya ga wannan magana abar bincikawa ce saboda shi ne uban wannan tsarin mulki da ya maida Arewa fifa – iya – koma baya. Dr. Imam bai yi wata-wata ba, sai ya fexe mai biri har wutsiya, a inda ya ce:

> *Ban yi tsammanin akwai Sarakunan da suka fahimci abin da Turawan Mulki ke buqata ba ko kuma manufar tsarin mulkin. Don a zaton su idan suka faranatawa Razdan ko Di'o rai, to, komai ya yi kyau buqata ta biya babu kuma sauran abin yi. Annan sai Gwamna Lugga ya ce da shi, Wato basu san farantawa talakawa ita ce hanya mafi kyau da za su farantawa Razdan ba? Imam ya ce: 'A'a, ai duk hankalinsu na kan Turawan mulki ne ba jama'arsu ba. Saboda haka sai suka shiga cikin haxarin rasa samun amincewar jama'arsu ba tare da sun farga da illolin da yin hakan ya qunsa ba.*
>
> *A wancan tsohon zamani', ya, ci gaba da bayani, "Sarki na da qarfin iko idan yana da goyon bayan baraden Majalisarsa. Amma a*

---

[1] *Ibid.*, shafi na 34.

[2] Abdurrahman Mora, *Memoir of Abubakar Imam*, shafi na 77

yanzu da yawa sun watsar da Majalisarsu saboda sun samu goyon bayan Razdan don haka basu buqatar goyon bayan kowa. Mutane da yawa na tunanin cewa yanzu da zuwan Turawa Sarakuna na samun ilimi amma da can suna mulkin kama karya da zalunci ne. Haka kuma talakawa da wasu qalilan masu ilimi na cewa idan Sarki na son ya azabtar da mutum sai ya cinna masa Razdan ya ce masa wannan lalatacce ne ba shi da ladabi da biyayya. A irin wannan hali kuma sai aka lura bai kamata a kai qara kai tsaye zuwa ga Razdan ba domin sai ya turo maganar zuwa ga Sarki. Duk wani qoqarin xaukaka qara kuwa can ta ci tura saboda haka ba shi da amfani. A dalilin haka ne jama'a ke ganin suna qarqashin muxlaqin mulkin Sarki ne na Wahadahu La Sharika Lahu, duk da cewa suna jin suna qarqashin inuwar kariyar Razdan ne. Amma saboda irin wannan dangartakar da ke tsakanin Sarakuna da Razdan ya sa jama'a basu da wani 'yanci da sawaba da Mulkin Mallaka aka ce zai ba su.[1]

Tsarin *Indirect Rule* sai ya zamewa Arewa wandon qarfe, wanda ba a sa shi a yi tsaye ba a sa shi a zauna. Ya kuma zame mata kamar ciwon qanjamau wanda ya karya mata nagarta da azama sa'an nan ya wargaza kan al'ummarta. Tunda aka garqamawa Arewa mulkin *Indirect Rule* a shekarar 1903, abin takaici shekara hamsin da samun mulkin kai, amma ta kasa kumari. Haka kuma Turawan Mulki suke so su yi, don haka kuma suka aiwatar da wani shiri da ya maida Arewa fifa-iya-koma-baya. Wannan tsarin mulki ne kuma ya haddasa ya kuma assasa gaba a tsakanin Sarakuna da 'yan Kwaleji wato masu ilimin zamani a wancan zamani. Shi ne kuma ya haifar da gabar da ke tsakanin Sarakuna da 'yan Siyasa har yanzu.

Hasali ma dai, shi ne ya farraqa talakawa da Sarakunansu, ya kuma bar `yan siyasa na cin karensu ba babbaka. Haka kuma wannan mummunan tsarin mulki shi ya haifar da mummunan matsayin da talaka ya samu kansa a yanzu, inda `yan siyasa suka yi masa mugun riqon sakainar kashi, na yi masa mulkin garari, ko ya jefa quri'a ko kar ya jefa. Saboda quri'arsa bata amfanin komai. Kada a manta a wannan lokaci Sarakuna na cikin tsaka mai wuya don kuwa Razdantai ke mulki ba Sarakuna ba. Razdan ne ke tafiyar da muxlaqin mulkin ba Sarki ba. Wannan ai shi ne tsarin mulkin *Indirect Rule*. Don haka sai Razdan ya fake da guzuma ya harbi karsani. A kuma wannan tsari Sarki na tafiyar da mulki ta bin umarnin Razdan amma ba Majalisar Sarki ba. Daga qarshe don ya qara jin mummunan tasirin wannan tsari, sai Gwamna Lugga ya tambaya, " Ina matsayin Majalisar Sarki ?" Dr. Imam ya ce da shi:

---

[1] Abdurrahman Mora, *Memoir of Abubakar Imam*, shafi na 78

"Jama'a sun san 'yan Majalisar Sarki ke zavansu kuma ba sabin umarnin kowa sai nasa. A duk zaman Majalisa, Sarki ke tafiyar da komai, duk 'yan majalisa da Kansiloli babu mai ra'ayin kansa sai na Sarki. "[1]

Wani mummunar illar *Indirect Rule* shi ne ya taimaka wajen assasa tasirin raba kan jama'a da Turawa suke shiryawa Arewa. A dalilin haka ne Dr. Imam, ya ce: "Mutane yanzu an kasafta su zuwa azuzuwa uku; "Sarakuna, da Ma'aikata da Talakawa."[2] Wato wannan tsarin mulki da tsarin ilimin boko sun taimaka wajen shimfixa tsarin rayuwar al'umma irin na Jajmananci, wato Hindu *Caste System* ga al'ummar Musulmin Arewa.

Lord Lugard ya nemi ya xora laifin ga Sarakuna wanda ya ce akasarinsu basu da ilimin zamani. Amma sai Alhaji Abubakar Imam ya kare Sarakuna, inda ya ce, ko da ba su da ilimi Sarakunan mu masu kaifin basira ne. In suka ga dama za su yi shugabanci mai kyau ta aiki ba ta kwakwazo ba. Ni, a ra'ayina Turawa ne ke da laifi. Domin akasarinsu basu fahimce mu ba, yawancin mu kuma bamu fahimce su ba saboda a bisa wasu dalilai ba sa ma son su yi cuxanya damu. A bisa gaskiya akwai karin magana da ke cewa,"ba rashin sani ke da illa ba, sai lalataccen ilimi, ta yaya za mu fahimci juna tunda babu kyakkyawan dangartaka? Ai dangartakar Bature da xan Arewa, kamar ta yaro ne da ubangidansa. Babu abin da ke tsakaninsu sai yaro ya riqa bin umarnin ubangidansa . . .[3]

Sir Bryan, ya yi tsokaci akan wannan lamari inda ya ce: "Da yawa cikin soke soken da ya yi mana, ya rubuta, ya aika wa Gwamna Lugga waxansu soke soken namu a cikin Gaskiya Ta Fi Kwabo a jerinsa na Edita. Waxannan soke soke da ya yi, bai tsaya a kanmu ba, har ya ci gaba da su kan Sabon Shirin Mulki da gwamnatin Nijeriya ta shirya. Yana cewa wai an yi rabon kura. Wai a cikin tsarin duk bai ga wurin da aka ba talakawa qofa ba ta yadda za aji ra'ayinsu.[4]

Babbar sukar da ya yi ita ce da ya cewai bai ga qofar da aka buxa wa 'manyan gobe' ba, balle su ma aji ra'ayinsu. Manyan gobe su ne 'yan'uwansa waxanda suka yi makarantar Turawa. Wannan suka da Abubakar Imam ya yi, ta girgiza tunanin shugabanni a Ingila. Domin kuwa ta sa an juye abin da ya rubuta da Hausa cikin Turanci, aka faxe shi a cikin Rediyon Ingila, wato (B.B.C). Abubakar Tafawa Valewa sa'an nan yana makarantar jami'a a Ingila, shi aka sanya ya fassara soke

---

1 *Ibid*.

2 Abdurrahman Mora, *Memoir of Abubakar Imam*, shafi na .

3 *Ibid*.

4 Abubakar Imam, *Auren Zobe*, shafi na 34.

soken daga Hausa zuwa Turanci, kuma shi aka sanya ya karanta Turancin a cikin Rediyon Ingila."[1]

Duk namijin qoqarin da Dr. Imam ya yi wajen nuna illolin da *Indirect Rule* ya haddasawa Arewa bai girgiza shugabannin Arewa ba amma ya girgiza Shugabannin Ingila. Dalilin da ya sa shugabannin Arewa suka qi fuskantar illolin *Indirect Rule* saboda suke amfana da su har yanzu. Arewa ta kasa sauyawa ta tafi da zamani har yanzu saboda an kasafta al'ummarta zuwa azuzuwa uku." Sarakuna da Ma'aikata da Talakawa." Wato an kafa tsarin al'ummar Hindu a Nijeriya ta Arewa ta hanya ba da ilimin boko wanda yake xauke da bigiren Hindu. Saboda haka babu yadda za a yi Arewa ta sauya da zamani.

Illar *Indirect Rule* mafi muni shi ne ya maida Musulmin Arewa, "Musulmi da halin Hindu. A cikin wannan tsari ne Almajirai (masu neman ilimin Alqur'ani mai Tsarki) su ka zama "untouchables" wato kasqantattun al'umma. Su ne a aji na huxu, su ne kuma mafi yawa. A wannan zamani Sarakuna an sagale su a ragaya domin, wannan illar tayi tasiri sosai akan Musulmin Arewa. A dalilin haka ne masifu iri-iri ke hudo kai a Arewa, jama'arta kuma ke cikin qunci da talauci da mayata. Abin da 'yan Kudu ke yi sai guxa suna cewa, "Talauci ya yi katutu a Arewa."

[1] *Ibid*., shafi na 34

KASHI NA GOMA SHA-TARA

Cibiyar Yaxa Addini

Kaduna Bariki

Da Turawa suka ci qasar nan sun yi qoqarin kashe Addinin musulunci kwata-kwata musamman a Arewacin wannan qasa. Idan aka yi la'akari da wannan mugun shiri da karan tsanar da Turawan suka xana wa Addinin musulunci, sai a gane dalilin tavarvArewar Addinin musulunci da farko a garin Kaduna, wanda yake tushen mulkin Turawan mallaka. Ka ga wato mazauna garin dole su taso da muggan xabi'un da Turawan suka dasa, wannan kuma zai sanya su yi wa addininsu xaukar sakainar kashi.

Muggan xabi'un Turawa sun yi kaka-gida a wannan lokaci har mutanen garin suka yi dumu-dumu a cikinsu, abin, abin qyama. Saboda Kaduna Bariki ce. Haka ma garin Jos da Turawa suka kafa a shekarar 1914. Kusan kowane irin iskanci da barikanci da sharholiya daga garin Kaduna ya samo tushe, an yi shekara da shekaru ba ka jin maganar addini, sai dai ga waxanda Allah Ya kuvutar, waxanda suke ba su da yawa.

Saboda irin wannan hali ne ya sa, 'yan wannan gari suka yi qaurin suna wajen iskanci da aikata masha'a, inda har an kai lokacin da suka zama abin qyama ga sauran mutanen Arewa. Wani mawaqi a cikin waqarsa ta garuruwa, ga abin da yake faxi kamar haka:- *Kaduna wa Jos Dama Yaskunha Yakunu Shaqiyan Sharibal Khamri Asiyyan*. Ma'ana shi ne Kaduna da Jos wanda ya zauna a wannan wuri zai zamo shaqiyi mashayin giya mai savon Allah! Kafa Bariki na xaya daga cikin shirin Mulkin Mallaka. Domin daga waxannan garuruwa ko barikoki ne za su zama cibiyoyin watsa xabi'u da al'adun Turawa ga sauran qasashe.

A shekarar 1952 Kaduna ta yi baquncin wani babban mashahurin malami wato Sheikh Ibrahim Nyass wanda ya sauka a gidan Ciroman Kano, Alhaji Muhammadu Sunusi da ke kan titin Kano a Sabon Garin Doka. Wata qila wannan gari ya baiwa Shehun sha'awa don ya tambaya ya ce, "ya ya sunan wannan gari?" Sai jama'a suka amsa "Kaduna." Ita wannan kalma da Larabci tana nufin "kamar baya" Saboda haka sai Shehun ya ce, "Kaduna Laisa duna." Wato Kaduna ba baya take ba. Shehun Malamin ya yi amfani da ma'anar Kaduna amma sai ya bata kyakkyawan fassara. Mashahurin Malamin ya fassara hikimar haka da "kafu tasbih," wato kamar abu amma ba abun bane. [1] Kaduna a gaba take ba a baya ba! Ko da yake a wancan lokaci Kaduna a baya take a harkokin addini amma kuma ba

[1] Hira da Malam Nazifi Ahmad Hafizi, 13. 10. 2008

a baya take! Bayan shekaru talatin sai ga hikimar wannan mashahurin malami ta bayyana. Sai garin yake kan gaba wajen harkar Addinin Musulunci.

Amma tun fil-azal Allah Ya yi wa wannan wuri da aka kafa garin Kaduna albarka da kyakkyawan usuli, domin an yi mashahuran malamai a wurare daban-daban a wannan waje tun kafin vullowar Turawa, kamar yadda aka ba da labari a baya. Saboda haka ba abin mamaki ba ne ganin Kaduna da take bariki ce, da farko a zamanin Turawa ta zama babbar cibiyar yaxa Addinin musulunci wanda kusan ba shi da na biyu a Nijeriya baki xaya. Wannan ya zo dai-dai da wani lokaci na wayewa game da addinin Annabi Muhammadu (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi), wanda ba Nijeriya kaxai ya shafa ba, a'a duk duniya baki xaya. A kusan a ko'ina a duniya yanzu Musulmi sai gwagwarmayar neman kafa shari'a ko mulkin Islama suke yi a qasashensu.

Da qurar juyin Islama ta taso a kusan qarshen qarni na ashirin daga Iran a shekarar 1979, ta kuma bugo zuwa Nijeriya sai ta murtuke a garin Kaduna a cikin 'yan shekarun nan. Murtukewar sha'anin addini a garin Kaduna, sai ya zama gagarumin haske ga mazauna cikinta don sun farga sun kuma tashi tsaye wajen karatu tare da neman ilimin Addininsu. Wannan hali sai ya wanke masu qaurin sunan da suka yi wajen barikanci.

Akwai wasu dalilai waxanda suka taimaka wajen mayar da garin Kaduna babbar cibiyar Addini. Matsayinta na fadar Arewa, ya sa duk wasu abubuwa da suka shafi mutanen wannan Jihar, to, a Kaduna ake yin shawarwari tare da xaukar matakan gyara su. Haka kuma shigowar makarantun Islamiyya a wannan gari sun taimaka gaya wajen karantar da Addinin musulunci, waxannan makarantu ne suka taimaka wajen kafa qungiyoyin addini daban-daban a wannan gari.

Har ila yau kafa Qungiyar Jama'atul Nasril Islam a wannan gari, ya sa duk abubuwan da suka shafi Addinin musulunci, to, sai sun zo ga wannan qungiya, aikace-aikacen wannan qungiya kuma daga garin Kaduna ake tafiyar da su. Vullowar Qungiyoyin Addinin musulunci da rikice-rikicen da ke varkewa a tsakanin Musulmi ta savanin aqida sun taimaka wajen fito da garin Kaduna ga idanun duniya. Daga qarshe kuma akwai kyakkyawan harsashi game da Addini da mazauna garin suka kafa tun a shekarun baya wanda ya taimaka sosai wajen tafiyar da harkokin addini a garin Kaduna a yanzu, misali kamar kafa makarantu da gina masallatai.

Wani mashahurin malami xan mashahurin malami, mai suna Malam Hassan Surajo tare da qaninsa Malam Awwal Surajo ne suka fara kafa makarantar Islamiyyar a wannan gari, ta yadda ilimin musulunci a Arewa zai tafi da zamani. Amma sai Malam Hassan ya bar wa qaninsa sabgar wannan aiki saboda qwazo da kuzarinsa. Dukkansu 'ya 'yan Malam Surajo ne wani mashahurin malamin malamai kuma malamin Sarakuna wanda ya yi suna a zamaninsa. A lokacin da

Malam Awwal ke fafitikar kafa makarantar Islamiyyar farko a Kaduna ya samu goyon bayan attajirai da malamai da shugabannin Kaduna a wancan zamani.

A cikin ginshiqan gina harsashin Addinin musulunci a garin Kaduna tun a wancan lokaci, da iskanci da sharholiya suka yi kaka-gida, akwai wani babban attajiri wanda ya yi abin da tarihi ba zai tava mantawa da shi ba. Shi dai wannan attajiri mai suna Alhaji Audu Kwangila, yana xaya daga cikin waxanda suka ba da kyakkyawar gudunmawa don yaxa Addinin musulunci a garin Kaduna. Alhaji Audu Kwangila shi ne mutumi na farko wanda ya fara ba da gidansa domin a kafa makarantar Islamiyya a Kaduna.

An haifi wannan bawan Allah karimi, Alhaji Audu Sulaiman a garin Ebba da ke kusa da Bida a shekarar 1907. Ya zo garin Kaduna a shekarar 1935, inda ya kama aikin kwangila da ma'aikatar jiragen qasa wato "Nigerian Railway Corporation," Saboda haka ne ma aka yi masa laqabi da Audu Kwangila. A cikin xan qanqanin lokaci sai arziqinsa ya bunqasa sosai.

Shi dai wannan mutumi, Allah Ya yi shi mutum ne karimi wanda ba shi da na biyu a duk faxin Kaduna wajen kyauta da taimakon jama'a a zamaninsa. Allah Ya yi shi mutum ne mai son xaukaka Addinin musulunci, mai sha'awar hulxa da manyan malamai da almajirai waxanda yake taimaka masu ta hanyar ba su masauki. Shi ne mai masaukin manyan malamai waxanda ke zuwa Kaduna lokaci-lokaci. A gidan Alhaji Audu Kwangila ba a sauke tukunya saboda ximbin baqin da ake samu a ko yaushe, saboda haka gidansa sai ya zama kamar na wani qasaitaccen basarake.

Saboda mu'amalarsa da malamai da kuma Larabawa masana ne, sai ya haxu da mashahurin malami Awwal xan Malam Surajo wanda ya fito da niyyarsa ta buxe makarantar koyar da Addinin musulunci, wato Makarantar Islamiyya tun cikin shekarar 1950. Alhaji Audu Kwangila ya lura da yadda garin ke bunqasa kuma Makarantun Allo inda yara ke koyon karatun Alqur'ani ba su da yawa, galibin malaman waxannan makarantu 'yan cirani ne, da cewa damina ta faxi sai ka neme su ka rasa sun koma garuruwansu sai kuma wata shekara mai zuwa. Kafa makarantun Islamiyya shi ne zai yi maganin wannan abu. A wannan zamani babu makaranta fitacciyar kamar makarantar Malam Surajo.

Ba wai makarantun Addini ne suka yi qaranci a wannan lokacin ba, har ma da masallatai. Saboda hanzari da bunqasar da Kaduna ta yi, sai Masallacin Juma'a na farko da ke kan layin Kano, ya yi wa Musulmi qanqanta sosai, saboda haka Alhaji Audu Kwangila da sauran jama'ar Musulmi suka taimaka wajen qara faxaxa masallacin da kuma qawata shi da fitilu da fankoki. Sardauna Ahmadu ne ya aza harsashin sake faxaxa wannan masallaci, a wani qasaitaccen biki da aka yi. Bayan an kammala gyare-gyaren masallacin ne, sai Alhaji Sir Ahmadu Bello ya gayyaci limamin masallacin Madina Sheikh Abdul'Aziz ya buxe shi a lokacin da babban limamin ya zo Nijeriya don buxe masallacin Sultan Bello da ke Sakkwato.

Wannan Masallacin Juma'a shi ake amfani da shi har yanzu yana kuma xaukar xaruruwan Musulmi a lokacin ibadarsu.

Wajen taimakon gajiyayyu kuwa, kusan a ce Alhaji Audu Kwangila ya fi kowa a zamaninsa. A kowane lokaci jama'a iri-iri za ka ga suna kaiwa da komowa a gidan wannan attajiri, ba domin komai ba sai don neman taimako. Allah Ya azurta Alhaji Audu Sulaiman da 'ya'ya masu yawa, ya rasu a cikin shekarar 1979. Allah Ya jiqansa ya rahamshe shi, amin summa amin. Kafin ayi bayanin yadda aka kafa makarantar Islamiya ta farko a Kaduna sai a ba da xan taqaitaccen tarihin makarantar Islamiyyar farko a Arewa.

Makarantar Islamiyyar Farko a Arewa

Qasaitaccen mutumin da ya buxe makarantar Islamiyyar farko a Arewa shi ne Dr. Abubakar Imam. Shi ne ya ba da labarin yadda aka kafa wannan Makaranta. Ya ce a shekarar 1948, wani xan Kasuwa da ke zaune a Kurmi, wato Jihar Yamma, mai suna Alhaji Gambo Sawaba ya je wajen Dr. Imam a matsayinsa na Editan mashahuriyar Jaridan nan ta Gaskiya Ta Fi Kwabo wadda sharhohinta da labaranta ke wayar da kan jama'a matuqar gaske, don haka ne ya zo ya nuna godiyarsa ga irin gudunmawar da Edita da jaridarsa ke bayarwa a Arewa. A wannan lokaci ne sai Alhaji Gambo Sawaba ya zo masa da kukan 'yan Arewa da ke zaune a Kurmi su ke yi, na rashin samun makarantar da za su riqa kai 'ya'yansu don su koyi Karatu da Ilimin Addinin musulunci. Saboda haka ne suka turo shi takanas zuwa wajen Dr. Imam don ya taimake su ya gina masu makarantar da za su riqa koyadda ilimin Addinin musulunci da ilimin boko baki xaya. Wannan roqo na al'ummar Musulmin Arewa da ke zaune a Kudu ne ya haifar da kafa Makarantar Islamiyya a Arewa.

An yi wannan zance a gidan shahararren Balaraben Malamin nan mutumin qasar Mauritaniya, mai suna Alhaji Baba Ahmed da ke zaune a Tudun-Wada Zariya. Shi Alhaji Baba Ahmed Balarabe ne mutumin qasar Mauritaniya wanda ya zauna a Tudun Wada dake Zariya ya qara bunqasa ilimi a birnin Zazzau da sauran qasashe a Arewa. Waxannan qasashe kuma sun qaru da ilimi da hikimar mulki da havakar makarantu. Tun a shekarar 1944 yake bada labarin yadda qasarsa ke baiwa malamai da makarantu muhimmanci sosai. A kan maganar makaranta malamin ya bada labarin cewar:

"Ai mu a qasarmu babban aikin Sarki shi ne, kula da makarantu, Sarki a wajenmu ba shi da xa sai xan makaranta, sauran ayyuka duk a gare shi a bayan aikin makaranta suke. Ya iya bar wa Majalisa waxxannan ayyuka, banda kula makaranta. Wannan aikinsa ne na kansa.

"Yaro, namiji da mace, tun suna 'yan shekaru huxu suke makaranta suna karatun Larabci da na zamani! Ran da yaran babbar makaranta za su fita, sai Sarki

ya hawo da Sarakunan sa, da iyayen yaran da ke makarantar duka, su zo makarantar. Wakilin makarantar ya jawo takardun shaidar aikin yaran a karanta xai-xai a gaban taro, sa'an nan yaran da suka sami takardar kyawun aiki (Satifiket) a ba Sarki ya ba su.

"Daga nan sai Sarki ya ce 'Ku waxannan yara da kuka yi qoqari kuka sami takarda, sai ku zo gidana. Yau, da gode, da jibi, duk ku baqina ne. Kowannenku kuma na yarda ya taho da abokansa.'

"Yaran nan su tashi da murna, su bi Sarki, ya je ya saukar da su a gidansa ya yi ta yi musu dina har kwanaki uku. Daga nan sai misali Waziri ya ce, 'Ni ma na xauki baquntarku kwana guda!' duk manyan Sarakai na farin ciki ga xaukar yaran nan. Daga nan sai a sallame su, su kama ayyukansu.

"A qasarmu, wannan yana qara wa yaran makaranta da malamansu himma. Kuma ta haka, iyaye sai su qara matsa wa 'ya'yansu don gudun kar su ba su kunya ranar taro!"[1]

A kan irin wannan tarbiyyar Larabawan Mauritaniya Alhaji Baba Ahmed ya ginu don haka yake da azama wajen ayyukan makaranta da yaxa ilimi. A kan waxannan ayyuka ne ya sadaukar da rayuwarsa xungum. Shi ma Alhaji Abubakar Imam mutum ne wanda ya yi ficewajen harkar ilimi da wayar da kan jama'a. Saboda haka abutarsa da Alhaji Baba Ahmed ta dace sosai. Wataqila ma harkar ilimi suke tattaunawa a lokacin da Alhaji Gambo Sawaba ya zo da wannan muhimmin saqo. Ka ga ke nan abin nema ya samu!

Samun wannan saqo da Alhaji Dr. Abubakar Imam ya yi, saboda shahararsa ya sa shi murna da farin ciki wanda har ya kusa ya zubar da hawaye. Sa'an nan kuma ya ga an xora masa wani nauyi babba a kansa. Saboda haka ba tare da vata lokaci ba sai ya nemi shawarwari Alhaji Baba Ahmad wanda shi ma ya yi fice a Arewa wajen qarfafa yaxa harkokin Addinin musulunci. A wannan lokaci sai mashahurin malamin ya qarfafa zuciyar aminsa ya kuma ba shi tabbacin ba shi goyon baya xari bisa xari akan wannan qalubale da ya samu, wajen kafa wannan makaranta ba tare da vata lokaci ba.

Da la'asariyar wannan rana sai Alhaji Dr. Abubakar Imam ya tattauna batun kafa makarantar da wani attajiri da ke Zariya mai suna Alhaji Shafi'i. shi ma bai vata lokaci ba wajen ba da taimakon kuxi don kafa wannan makaranta. Haka kuma wannan attajiri ya ce zai ba da yara bakwai daga unguwarsa don shiga wannan makaranta. Saboda haka da waxannan yara, da 'ya'yan Dr. Abubakar Imam da 'ya'yan Alhaji Bala Ahmad sai aka buxe wannan makaranta a gidan wannan mashahurin Edita.

[1] GTK, Disamba 1944, shafi na 6.

A cikin xan qaramin lokaci har an sami rajistar yara ashirin. Saboda haka sai Dr. Alhaji Abubakar Imam ya tuntuvi wani mashahurin malami abokinsa mai suna Alhaji Haliru Binji wanda aka turo Kwalejin BArewa a matsayin Malamin Larabci a shekarar 1949, domin ya rubutawa wannan makarantar tsari da manhaja. Abin nema ya samu, Malam Haliru Binji ya karvi wannan aiki da hannu biyu ya kuma ba da shawarwari da a xauki wani malami da ke zaune a Unguwar Kakaki da ke cikin birnin Zariya mai suna M. Shu'aibu Usman. Bayan an gana da wannan Malami, sai aka xauke shi aikin koyarwa akan albashin fam uku a wata. A zauren gidan Editan aka riqa koyarwa a wannan makaranta. An kuma sami fahimtar malamai da iyayen yara sosai wajen tafiyar da makarantar. A dalilin haka sai ta shiga havaka cikin hanzari.

A dalilin haka ne sai Alhaji Shafi'i da Malam Haliru Binji da Alhaji Dr. Abubakar Imam suka yi niyyar gina azuzuwa, Alhaji Abubakar Imam sai ya sayi filotai guda uku, inda aka gina zauren makaranta guda; aka gina xakin girki da wajen cin abinci da guda, sauran filotin kuma aka gina mazaunin xalibai da shi. Wato dai an kafa makaranta ke nan. Saboda haka sai daga ranar 10 ga Oktoban shekarar 1950 Miladiyya wanda ya yi dai-dai da 1 ga watan Muharram 1370 A.H, aka riqa kiranta Makarantar Islamiyya, bayan ta tare a sabuwar harabar makaranta.[1]

Wannan ita ce makarantar Islamiyya ta farko a Arewa. Wannan makaranta ta zo da sabon abu wanda shi ne koyar da ilimin Addinin musulunci da ilimin boko. Saboda a wancan zamani makarantar allo da makarantar boko a rabe suke ba a gwamasu. Amma sai ga shi an gwamasu waje guda, ana kuma tafiyar da su baki xaya. Idan sabon abu ya zo, mutane za su riqa xar-xar da shi kafin su fahimce shi sosai. A hankali sai wannan makaranta ta riqa havaka cikin hanzari tana samun xalibai daga sassan Kudu da Arewa har ma da qetare.

Saboda ita wannan makaranta tana koyar da karatun Alqur'ani da ilimin Addinin musulunci sai malamanta da iyayenta suka riqa wallafa litattafai waxanda za su taimaka sosai wajen cimma manufofin wannan mashahuriyar makaranta.

A wannan lokaci ne Alhaji Dr. Abubakar Imam ya wallafa *Tarihin Annabi* (mai sifili huxu), ya kuma kammala sifili na huxu na *Tarihin musulunci*. Shi kuma M. Haliru Binji ya wallafa littafin *Ibada da Hukunci* (Littafi na xaya da na biyu) da Mu Koyi *Larabci*. A wannan lokaci ne M. Na'ibi Suleiman Wali na aiki da Norla a Zariya, shi ma sai ya taimaka da wallafa littafin *Mu Koyi Ajami* da *Tauhidi a Sauqaqe*. Sauran litattafan da ya wallafa sun haxa da *Tarbiyya ga Mutum*, da *duniya Ina Za Ki Da Mu* da *Mu Koma Kan Hanya;* shi kuma Shugaban wannan makaranta, M. Shu'aibu Usman, sai ya wallafa littafin *Addini a Sauqaqe,* da *Mu Qara Kyautata Addininmu*. Alhaji Baba Ahmad kuma sai ya

[1] Abdurrahman Mora, *Memoir* of *Abubakar Imam*, shafi na . 189-190

wallafa littafin *Almajiri Da Malami* da *Masu Hikima Sun Ce* da *Matambayi Ba ya Vata*.[1]

A wannan lokaci kuwa akwai qarancin litattafan koyar da Addinin Musulnci a Arewa baki xaya. Saboda haka sai wannan makaranta ta qara assasa wallafa littattafai masu amfani sosai, waxanda suka taimaka gaya wajen bunqasa ilimin Addinin musulunci ba a Arewa ba kai harda nahiyar Afirka baki xaya. Haka kuma ita wannan makaranta ta qara haskaka birnin Zariya wajen ilimi da taqawa. Ta kuma zama abar koyi a duk lardunan Arewa.

A ran 22 ga Mayun shekarar 1952, aka yi babban taro a wannan marakarantar saboda ba 'yam makarantar hutu, wanda aka saba ba su kowace shekara. Iyayen yara na Zariya sun halarci wannan wuri. Iyayen makarantar wato M. Abubakar Imam da Alhaji Shafi'i sun gayyaci jama'a da dama, har ma da Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu. Amma bai sami damar halarta ba saboda a lokacin ne zai tafi Kaduna, wajen Taron Sarakuna. Cikin manyan mutane da suka halarci wannan taro har da Mr. Peter Achimugu xaya cikin wakilan Kabba, da kuma Sarkin Tudun-Wada.

Kafin a ba su wannan hutu, sai da yaran nan suka yi wata waqa ta Larabci mai qayatarwa. Duk dai yawanci irin abin da aka koya musu, an sa su sun yi a gaban jama'a. A wannan makaranta da akwai yara xari da ashirin waxanda su ke rubuce. Amma duka duka waxanda su ke zuwa su xari da hamsin ne.

A cikin wannan makaranta akwai yara da suka zo daga Ikko, da Anicanhar ma daga qasar Saliyo wasu 'yam Makarantar ke zuwa. Ana koyar da ilimin Addinin musulunci da ilimin boko mai zurfi. A wannan ranar bikin samun hutu sai Alhaji Ali Maimesa na Tudun-Wada Zariya ya miqe ya ce, "tun daga yau 22 ga watan Mayun shekarar 1952, am ba 'yam makaranta hutu, ba za su dawo ba, sai 10 ga watan Salla, wato 3 ga watan Yuli ke nan. Daga nan aka sallami yara. Daga nan sai M. Abubakar Imam kuma ya miqe ya yi jawabi. A cikin jawabinsa, sai ya qarfafa wa iyaye su riqa biyan kuxin makaranta da wuri. Malaman wannan makaranta su ne, M. Shuaibu Zariya, da M. Aminu Hikima Kano, da M. Mamman Kusherki."[2]

Saboda ganin amfanin da wannan makaranta ke da shi ga jama'ar Arewa, sai gwamnati ta riqa ba ta tallafin kuxi don ta ci gaba da harkokinta. Mai girma Sarkin Zazzau Alhaji Muhammadu Aminu sai ya ba da isasshen filli a shekarar 1960 inda aka gina harabar makarantar ta dun-dun-dun. Wanda ya lura da ginin makarantar shi ne Alhaji Muhammadu Wali. Daga nan sai aka sanya wa Makarantar suna "Nurul Huda Primary School". An yi shagalin biki wajen aza harsashin wanna makaranta.

---

[1] Abdurrahman Mora, *Memoir* of *Abubakar Imam*, shafi na . 189-190

[2] GTK, 28 Mayu, 1952, shafi na 6

Ranar Lahadi ne Shugaban Hukumar Xaukar Ma'aikata ta Jihar Arewa, Alhaji Abubakar Imam da Alhaji Shafi'i suka aza tubalin harsashin ginin sabuwar Makarantar Islamiyya ta nan Tudun-Wadan Zariya, mutane masu yawan gaske kuwa sun halarci wannan shagalin aza tubalin gini. Daga cikin manyan mutanen da suka halarci wurin har da Marafan Sakkwato Alhaji Ahmadu Xambaba, da Alhaji Abubakar Tunau, Sakataren Kamfanin Raya Qasa na Jihar Arewa, da Alhaji Abdurrahman Mora, da sauran waxansu manyan 'yan kasuwa na Zariya.

Har ila yau, kafin ranar aza wannan tubalin gini kuwa, sai da Makarantar ta gayyaci iyayen yaran makarantar don su halarci wannan shagali na aza tubali da aka yi. Haka nan kuma an gayyaci 'yan kasuwa da ma'aikata masu ximbin yawa.

Tun da farko kuwa kafin a ci gaba da yin komai, sai da Alhaji Abubakar Imam ya fara aza tubalin, a lokacin da yake aza tubalin, sai 'yam makaranta suka shiga karanta Fatiha. Haka kuma a lokacin da Alhaji Shafi'i yake aza wani tubalin, a nan ma 'yam makaranta sun karanta Fatiha.

Bayan da suka qare aza tubalin ne, sai Alhaji Haliru Binji, ya yi wa jama'ar da suka taru don shagalin aza tubalin jawabi. A cikin jawabinsa, Alhaji Haliru Binji ya yi godiya ga gwamnati da ta ba wannan makaranta kuxi fam dubu biyar (£5,000), kamar yadda take ba waxansu makarantu, don ginin sabuwar makarantar Islamiyya ta Tudun-Wada.

Alhaji Haliru Binji kuma ya ce idan an gama ginin makarantar za a sami azuzuwa takwas, kuma makarantar za a sake mata suna. Ya ce yanzu akwai makarantu da yawa a Jihar Arewa ko ma a Nijeriya baki xaya waxanda aka san su da suna Makarantar Islamiyya. Saboda haka za a bambanta wa wannan makaranta suna. Za a riqa kiranta, "Nurul Huda."

Haka nan kuma ban da koyar da ilimin Addini da Larabci, makarantar za ta riqa koyar da 'yam makaranta ilimin zamani, wanda zai kai har ga zurfin ilimin aji bakwai na Babbar Firamare, wanda yake daga nan yaran makarantar suna iya xaukar jarabawar shiga Makarantun Sakandare da Makarantar Fasaha ta gwamnati.

Bayan Haka nan, Alhaji Haliru Binji ya bayyana godiya ga En'e ta Zariya, kuma ya ce sun sayi filin da za a gina makarantar kadada huxu da rabi a kan fam sittin da shida (£66) a wurin En'e. Ya kuma bayyana godiya ga mai kula da sha'anin gine-gine na En'e ta Zariya, M. Muhammadu Wule, saboda taimakon da ya yi wajen sha'anin aikin ginin wannan makaranta.

A qarshen jawabinsa, Alhaji Haliru Binji ya cewannan makaranta za ta riqa koyar da yara har da manya duka baki xaya. Wato idan yara sun yi karatu da safe, manya kuma za su riqa yin karatu da Yamma. Sa'adda ya qare jawabinsa, sai aka karanta Fatiha aka tashi.[1]

---

[1] GTK- 15 Ga Disamba 1961

Alhaji Shafi'i da iyayen yara xaliban wannan makaranta sun ba da taimakon kuxi wajen havaka ta. A wani taron iyayen xaliban da aka yi ne Alhaji Muhammadu Maqarfi da ke aiki a Hukumar Bitinariya wato *Veterinary Department* da ke Zariya ya ba da taimakon zunzurutun kuxi har fam ishirin (£20).[1]

Wannan mashahuriyar makaranta ta fidda xalibai masu yawan gaske, waxanda suka haxa da: Tukur Imam, da Ahmadu S. Musa, da Mustafa Muhtari, da Yusuf Usman daga Katsina, da Muhammadu Abubakar, da Abdu Namalama, da Safiyanu Baballe, da Umaru Yusufu. Daga bisani ne M. Salihu Kwantagora ya zama Malami a makarantar, ya kuma zama Hedmasta bayan Hukumar Ilimi ta Zariya ta karvi makarantar. Xaliban da wannan makaranta ta yaye sun riqe manyan muqamai a Arewa da qasa baki xaya.

Sauran xalibanta da suka zama manyan mutane sun haxa da: Dr. Muhammadu Saifuddin Mora, da Alhaji Halifa Baba Ahmed, da Alhaji Mamoon Baba Ahmad, da Alhaji Abubakar Abdulqadir da Qamarudeen Imam, da Alhaji Tijjani Musa Jos, da Alhaji Dada Ali Muhtari Kano, da Idris da Zainu Ali dukkansu a Zariya.[2]

Allah cikin qudurar sa ya kan azurta al'umma ta hanyar wasu bayinsa waxanda ya ba su baiwa iri daban-daban, kamar ilimin cuce-cuce da magani da sadaukantaka ta fannin yaqi ko kuma arziqi da karimci da dai sauran ire-iren baiwoyin da za su taimaki jama'a wajen wadata da ci gaba. (Allahu Akbar)! Allah Ya azurta garin Kaduna da attajirai karimai masu yawa a lokuta daban-daban, sun kuma taimaka gaya wajen havaka wannan gari.

Makarantar Islamiyyar Farko a Kaduna

Tsarin koyar da Addini da ilimin boko ta haryar Makarantar Islamiyya, tsari ne da ya zama asali daga Yarbawa Musulmin Jihar Yamma. A lokacin da ake qoqarin kafa wannan tsarin bada ilimi a Kaduna wanda Malam Hassan Surajo ke yiwa jagore, wani mashahurin Malami Bayarbe mai suna Imam Daniyalu Shitta Bey, shi ma ya bude Makarantar Islamiyya mai suna 'Ansarudden' a kan layin Abeokuta daura da layin Kano, a shekarar 1950. An cewannan makaranta ce ta qara wa Malam Surajo da kanensa Malam Awwal qarfin gwiwar kafa irinta.

A cikin shekarar 1950, Malam Awwal Surajo ya yi niyyar kafa makarantar Islamiyya a garin Kaduna. Amma tunaninsa ya bambanta da na sauran malaman zamaninsa saboda yana so ya haxa makarantar Allo da karatun Boko don ya murjesu su tafi gaba xaya. Wato samfurin koyar da ilimin addini da na boko irin na Yarbawa Musulmin Jihar Yamma. A wannan lokaci sai aka nemi taimako wajen Alhaji Audu Kwangila wanda bayan ya samu kyawawan shawarwari daga

---

[1] Abdurrahman Mora, Abubakar Imam Memoirs, shafi na 190

[2] *Ibid*., shafi na 191

manyan malamansa musamman Malam Ahmad Hafizi, don haka, sai ya bayar da xakuna guda biyar a gidansa da ke kan layin Abeokuta don a mayar da su azuzuwan karatu, ya kuma xauki nauyin biyan albashin malaman da aka danqa al'amuran wannan makarantar ta Islamiyya a hannunsu. Ita wannan makaranta mai azuzuwa guda biyar da ke layin Abeokuta a cikin sabon garin Doka, ita ce makarantar Islamiyyar farko a duk faxin Kaduna.

Malam Awwal Surajo shi ne jigon kafa wannan makaranta. Wannan malami xan Malam Sirajo ne, wani mashahurin malamin Kifaxi wanda ya taso daga garin Argungu ya komo Birnin Zariya da zama bayan ya samu karatun Alqur'ani da ilimi mai yawa a garuruwa daban-daban.

A lokacin da Malam Sirajo ke Zariya, ya shahara sosai har ya zama Babban Malamin Sarkin Zazzau Alu Xan Sidi, yana kuma xaya daga cikin shaqiqansa. Amma a lokacin da Turawa suka cire Sarkin Zazzau Xan Sidi daga kan gadon Sarauta a shekarar 1922, sai ya buqaci Malaminsa da ya komo Kaduna da zama, ya kuma aiko shi wajen abokinsa Rejimanci Malam Baqo wanda zai bashi masauki a garin Kaduna.

Malam Sirajo na isowa Kaduna sai Rejimancin Malam Baqo ya qarve shi da hannu bibbiyu ya kuma bashi masauki a cikin gidansa da ke kan titin Prince Edward. Daga bisani sun gane cewa suna da dangantaka a tsakaninsu saboda dukkansu Kabawa ne mutanen Argungu. Shi wannan mashahurin malami sai ya buxe babbar makarantar Alqur'ani a sabon garin Doka wadda ta yi suna wajen yawan almajirai da Karatu.[1]

Malam Surajo a matsayinsa na malamin Sarakuna, saboda haka ko da ya dawo Kaduna sai gidansa baya tsinkewa da jama'a manya da qanana. Manyan malamai, da Sarakuna da ma'aikata na kawo masa ziyara a kowane lokaci. Akwai wasu fitattn ma'aikata da ke yawan ziyartarsa kama. Malam Aminu Kano, da M. Isa Wali da M. M.D Yusuf da sauransu.

A dalilin haka ne ma Malam Aminu Kano ya shaqu da Malam Awwal Surajo. Saboda yana da ilimi mai zurfi da wayewa da gogewa wajen harka da jama'a. Tun a wancan zamani ne M. Awwal Surajo ke tafiye-tafiye zuwa qasashen Larabawa da Afirka don yaxa Addinin musulunci da neman ilimi. Malam Balarabe Qaya wanda ya zama gwamnan Jihar Kaduna ya yaba da qwazon wannan bawan Allah kuma sahibinsa.[2]

Saboda ganin irin wannan himma da qwazon M. Awwal Surajo ne sai Malam Aminu Kano ya shawarce shi da ya kafa makarantar Islamiyya a Kaduna. Malamin ya karvi wannan shawara. Kafin kace kwabo har an kafa 'yan kwamitin

---

[1] Hira da Malam Nazifi Ahmad Hafizi, ran 13 ga Oktoba, 2008

[2] Hira da Tsohon Gwamnan Jihar Kaduna Alhaji Abdulqadir Balarabe Musa, ran 20 ga Oktoba 2008.

kafa wannan makaranta shekarar 1950. Wata qila Malam Aminu Kano ya daxe yana burin kafa irin wannan Makaranta. Saboda an ce malaminsa M. Sa'adu Zungur ya so ya kafa irinta a garin Bauci amma bai samu goyon bayan yin haka ba. Domin Sarakuna na xar-xar da aikace-aikacensa a wancan lokaci.

Kwamitin malaman da suka xauki wannan nauyi kuwa ya qunshi Malam Muhammadu Mai Dala'ilu wanda aka fi saninsa da Malam Mamman Kano da Malam Isma'ila da Malam Lawal Abubakar da Malam Ibrahim Arab da Malam Nazee. Waxannan malamai su ne suka kafa tushen tafiyar da sha'anin Addinin musulunci ya tafi dai-dai da zamani a garin Kaduna, wato koyar da Addini daga Makarantun Allo zuwa makarantun Islamiyya. Huxu daga cikin waxannan malamai kuwa suna daga cikin waxanda suka fara yin karatu da kuma wa'azi a gidajen rediyo na Kaduna, don haka ba garin Kaduna suke karantarwar ba kawai har ma da duk sauran lungunan Arewa baki xaya.

Sauran malaman da suka koyar su ne: M. Yahya Abdullahi, da M. Balarabe Qaya, da M. Na'ibi Suleiman Wali, da M. Sale, da M. Adamu Ilori, da M. Tanko Wushishi, da M. Muhammad Musa, da M. Umar Xantsoho, da M. Tijjani Lukman da M. Mamman Kankiya. Saboda haka a fannin ilimin Addini da ilimin Boko, wannan makaranta nada qwararrun malamai.

A dalilin haka sai wannan makaranta ta yaye xalibai masu yawan gaske, tsofaffin xalibanta sun haxa da: Ali Ibrahim, da Aminatu Muhammad, da Salisu Ahmadu, da Muhammadu Badamasi, da Abubakar Muhammad Musa, da Rabi'u Baqo, da Fatimatu Ibrahim Arab, da Bilyaminu Sirajo, da Ruqayya Hassan Sirajo, da Nasiru Ibrahim Arab, da Abdulaziz Muhammad Musa, da Sa'idu Yusha'u, da Zakari Yusha'u, da Ibrahim Yusha'u, da Musa Yusha'u.

Sauran tsofaffin xaliban su ne: Muhammadu Kankiya, da Kaduna Audu Kwangila, da Kudu Audu Kwangila, da Kakuri Audu Kwangila, da Aminatu Audu Kwangila, da Lami Buda, da Khadijatu Bala Mai Awo, da Ahmadu Bala Mai Awo, da Mansur Jibrin, da Aminu Bala Mai Awo, da Mamman Ali Kacan, da Mai Kano Muhammadu Mai Gwari, da Uba Muhammadu Mai Gwari, da Ibrahim Muhammadu Mai Gwari, da Tsoho Muhammadu Mai Gwari.

Ali Ibrahim shi ne shugaban xali bai wato *Headboy* na farko, shi kuma Muhammadu Badamasi *Headboy* na biyu. Shugabannin makarantar su ne M. Yahya Abdullahi a matsayin Hedmasta na xaya da M. Abdulqadir Balarabe Qaya Hedmasta na biyu. A cikin qaramin lokaci sai makarantar ta havaka sosai, iyayen yara da Shugabanni na alfahari da wannan makarantar Islamiyya.

A lokacin da aka yi bikin buxe ta a shekarar 1952, an gayyaci manyan mutane masu yawa, sun kuwa halarci wannan biki. Babban baqo kuma shi ne Malam Ahmadu Bello Sardaunan Sakkwato. Malam Ahmad Hafizi ne ya buxe taro da addu'a, daga nan sai aka kira yara 'yan makaranta da su yi karatu. Xaliban da su

ka yi wa manyan baqi karatu sun haxa da: Ali Ibrahim, da Aminatu Muhammad, da Salisu Ahmad, da Abdulqadir Muhammad.[1]

Malam Ahmadu Sardauna da sauran manyan baqi sun ji daxin wannan karatu da yara su ka yi. Bayan haka ne Sardauna ya yi jawabi, inda ya godewa waxanda suka kafa wannan makaranta tare da iyayen yara da xalibai. Daga qarshe ya yabawa wannan makaranta ya kuma ba da gudunmawar kuxi fam hamsin (£50).

Tun daga kafa makarantar sai tasirinta ke qaruwa har ya zuwa shekarar 1954. A wannan shekara ce Mai girma Ciroman Kano Alhaji Muhammadu Sunusi ya sauki Sheikh Ibrahim Nyass a gidansa da ke Kano Road. A wannan lokaci sai manyan malamai ke zuwa suna gaida shi. Daga ciki akwai: M. Auwal Sirajo, xaya daga cikin almajiran wannan mashahurin malamin wanda kuma ya kafa makarantar Islamiyya ta farko a garin Kaduna. A wannan lokaci ne ma ya baiwa babban baqon kuma Gausul Zaman labarin Islamiyyarsa.

Saboda haka sai Sheikh Nyass ya buqaci a kawo masa xaliban wannan makaranta domin ya ji irin karatun da ake koya masu da zurfin iliminsu. A dalilin haka ne sai aka ga ya kamata akawo 'yan wannan makaranta don su karrama wannan mashahurin malami da karatu na fannoni masu yawa. Haka kuwa aka yi. Kamar yadda suka nuna gwanintar karatu da ilimi ga Sardaunan Sakkwato, haka suka nuna irin baiwar da Allah Ya huwace masu a gaban Sheikh Ibrahim Nyass da sauran malamai. Wannan Shaihi sai ya ji karatu fanni-fanni mai kyau daga bakin yara qanana. A dalilin haka ne ya albarkace su.

Sheikh Ibrahim Nyass ya yi farin ciki sosai da irin karatu da wannan makaranta ke koyarwa. Saboda haka ne ya umurci Malam Awwal Surajo da ya tafi gidansa da ke Kaulaha a qasar Senegal ya kafa irin wannan makaranta domin, ya karantar da 'ya'yansa. Wannan babbar xaukaka malam Awwal Surajo ya samu saboda ba kowane malami ne zai sami wannan babbar daraja ba. A dalilin haka sai ba tare da vata lokaci ba, ya tafi gidan wannan mashahurin malami, don ya karantar da 'ya'yansa. A dalilin haka ne ya kafa makarantar Islamiyya a gidan Gausil Zaman!

Makarantar Islamiyya wadda Alhaji Abubakar Imam ya kafa a Arewa ta tasirantu sosai saboda Sheikh Nyass ya albarkaci irin wannan sabon samfurin ba da ilimi, ya kuma buqaci a kafa irinsa a gidansa da ke Kaulaha. Malam Awwal Surajo wanda aka danqa wannan alhakki a hannunsa bai samu ta zama ba. Haka ya riqa zirga zirga a tsakanin makarantunsa biyu, xaya a Kaduna xaya, a Kaulaha har sai bayan shekara uku, Malam Awwal Surajo ya tare a Kaulaha a shekarar 1957.

Bayan da ya tare a gidan Sheikh Nyass, makarantar Islamiyya ta Kaduna ta riga ta kafu sosai. Saboda haka sai ta ci gaba da tasiri da bunqasa a garin Kaduna

[1] Hira Alhaji Salisu Ahmad Hafizi, ran 25 ga Oktoba 2008

da kewaye. Malaman ta sun tallafa wa ayyukan makarantar Islamiyyar dai-dai gwargwado. Malam Ibrahim Arab da Malam Najee su aka damqa wa jigilar aikin karantar da 'yan makarantar a fannonin Fiqhu da karatun Qur'ani tare da koyar da Larabci. Don makarantar ta tafi da zamani, sai aka xauki Yahaya Abdullahi da Junaidu Yahaya aikin tsara ayyukan darussa da koyar da karatun boko.

Makarantar ta taso da qarfi da kwarjini sosai saboda malaman da ke koyarwa a cikinta fitattu ne saboda sun haxa da ilimin boko da ilimin Addini. Kusan dukkansu sun sami babbar xaukaka da matsayi a gwamnatin Jihar Arewa. Alal misali, Malam Isa Wali ya riqe muqamin Akawun Majalisa a Majalisar Wakilai, ya kuma zama ambasadan Nijeriya a qasar *Ivory Coast*. Malam Balarabe Qaya, shi ne gwamnan Kaduna Alhaji Balarabe Musa. A wannan zamani ne Malam Junaidu Yahaya ya yi suna wajen riqon amana tare da gaskiya a aikin gwamnati akan bin qa'ida. Don haka ake masa laqabi da "Sufin gwamnati." Yana fara aiki a lokaci ya kuma tashi aiki akan lokaci. Haka kuma yana aiki tuquru kuma bil-haqqi da gaskiya. Ma'aikaci ne da ya nuna kyakkyawan misali wajen aiki ta aikata gaskiya ta furuci da alqalami.

Akasarin waxannan malamai, ma'aikatan gwamnati ne da suke amfani da wani lokacinsu wajen koyarwa. Sun kuma taimaka gaya wajen yaxa ilimin addini da ilimin addini da ilimin boko a garin Kaduna. Haka kuma sun xaukaka martabar makarantar a idon jama'ar tare da qara wayarda kan jama'a. Amma a lokacin da guguwar siyasa ta ta fara kaxawa sai aka sami rikicin siyasa a cikin wannan makaranta.

Iyayen Makaranta

Iyayen wannan makarantar Islamiyya da aka kafa a shekarar 1950 su ne: Malam Aminu Kano, da Malam Na'ibi Suleiman Wali, da Alhaji Isa Wali, da Alhaji M.D Yusuf. Waxanda suka taimaka gaya wajen kafa ta sun haxa da Malam Hassan Sirajo da Mai Buruji.

Malam Hassan Surajo shugaban wannan makaranta aminin Malam Isa Wali ne wanda yake fitaccene a Kano kuma babban abokin Malam Aminu Kano ne. A malaman wannan makarantar Islamiyya kuma akwai masu ra'ayin NEPU da yawa, basu kuma boye ra'ayinsu ba. Shi kuma mai makarantar Alhaji Audu kwangila amini ne ga Sardauna saboda haka shi mai ra'ayin NPC kuma wakilin wannan jam'iyya a Kaduna. Saboda haka ne kuma ba zai yarda wani abu ya shiga tsakaninsa da Firimiya ba. Saboda haka sai makarantar ta rabu biyu a bisa bambancin ra'ayin siyasa amma ba a kan addini ba. Saboda Sardauna na samun bunqasar wannan makaranta wadda 'yan NEPU suka kafa a Kaduna shi kuma mashahurin mutum ne da ba ya son ya zama na biyu wajen ayyukan alheri ga jama'a.

A dalilin rabuwar tsohuwar Makarantar, sai Malam Hassan Surajo ya kafa ta sa makarantar a layin 'Constitution', wadda ya sanya wa suna *Madrasatul Islamiyya Li Ansarul Islam* inda aka ci gaba da koyar da ilimin addini da karatun boko. A shekarar 1958, sai adireshin wannan Makaranta ya koma No. U,6 Katsina Road. Bayan ta yi shekaru uku a wannan wuri sai ta tashi ta koma Tudun-Wada a gida mai lamba G 1 Bachama Road a shekarar 1962. A nan ne ta ci gaba da habaka. Ita kuma makarantar Audu Kwangila ta ci gaba da aikinta. Amma dukkan makarantun ana kiransu ne da suna madrasatul Islama. Ita makarantar Audu Kwangila sai ta fi qasaita.

Makarantar Audu Kwangila

Vangaren makarantar da ke qarqashin Alhaji Audu Bida sai ta koma No 1, W.W. 20 Gumel Road a qarqashin jagorancin Malam Ibrahim Agaye wanda shi ne mataimakin shugaban wannan makarantar Islamiyya. A watan Oktobar shekaran 1958 wannan makaranta ta yaye yara goma sha-biyu da suka sauke karatun Alqur'ani Mai girma. Daga cikin su akwai yara maza goma sha-xaya da mace xaya.

Wannan makarantar sai ta ci gaba da havvaka a wancan lokacin tana da yara maza da mata da yawansu ya kai xari biyu da tamanin. Tana kuma da malamai guda shida waxanda suke koyar da fannonin ilimi daban-daban.

Saboda murnar bukin Mauludi da na saukar karatun Alqur'ani da 'yan wannan Makaranta suka yi ne sai kowa ya yi murna da farin ciki. A dalilin haka ne sai Alhaji Audu Kwangila ya sayo wa wannan makaranta na'urar qara sauti, *loud speaker* wato amsa amo domin yin amfani da shi a wannan makaranta.

Cikin ikon Allah sai makaranta ta qara havaka da kuma bunqasa sosai, iyayen yara suka shiga rububin sanya 'ya'yansu a *Madarasatil Isalamiyya* wadda aka fi sani da makarantar Audu Kwangila, saboda, haka sai azuzuwa biyar xin nan da ake amfani da su suka yi kaxan. Ganin haka sai Alhaji Audu Kwangila ya nemi hukuma ta ba shi fili don ya gina makaranta babba. Hukumar Kaduna ta amince da hakan ta ba shi makeken fili a fadamar rake da ke kudancin gari don gina babbar makarantar Islamiyya, amma daga baya sai aka canja masa wurin saboda ganin nisan wajen da kuma shirin gina filin wasa da Firimiyan Arewa, Alhaji Sir Ahmadu Bello yake yi a wannan fadamar rake, wato gina "Ahmadu Bello Stadium."

Hukumar Kaduna ta ba da fili mai faxin filotai huxu a cikin garin Doka a kan layin Ogbomosho domin gina wannan babbar makarantar Islamiyya. Aikace-aikacen gina makaranta babba, abin da kowa zai bayar da nashi taimakon ne, don haka sai aka nemi taimako daga jama'a don yin gagarumin wannan aiki, aka kuma samu. Sir Ahmadu Bello shi ne kan gaba wajen bayar da taimako, haka

kuma an samu taimako daga hukumar Kaduna da sauran jama'ar gari cikin hanzari.

Saboda samun isassun kuxin da aka yi, sai aka gina sabuwar makaranta mai azuzuwa guda biyu a shekarar 1963 zuwa 1964. An sanya wa makarantar suna "High Society." Shugabanin wannan makaranta ta "High Society" na farko su ne:- Alhaji Muhammadu Kusu, da Alhaji Muhammadu Kachan da Alhaji Ibrahim Arab, da Alhaji Abdul-Salam, da Alhaji Ahmadu Banufe da Alhaji Muhammadu Da'u Waita. Makarantar Audu Kwangila sai ta zama reshen wannan sabuwar makaranta.

Wannan sunan makaranta "High Society" ya kawo wata 'yar tangarxa tsakanin Alhaji Audu Kwangila wanda ya sanya mata sunan da sauran shugabannin makarantar. Dalilin wannan 'yar tangarxa kuwa, shi ne sunan "High Society" bai dace da makarantar ba saboda sunan wata taba sigari ce da take tashe a wannan lokaci. Ganin haka, sai shugabannin makarantar suka nemi a canja mata suna don bai kamata makaranta kamar wannan mai koyar da Addinin Islama, ta riqa amsa sunan taba sigari wato (High Society) ba. A dalilin haka aka sauya sunan makarantar zuwa Makarantar Shehu Abdullahi.

Makarantar Shehu Abdullahi

Maganar neman canja sunan makarantar, wato "High Society," ya turnuqe sosai har sai da shugabannin makarantar suka gurfana gaban Firimiya, Alhaji Sir Ahmadu Bello domin neman gyaran al'amari. Shi Kuma Firimiya ya damqa kwamitin da zai dubi wannan magana ga hannun Alqalin-Alqalan Arewa, Alhaji Abubakar Mahmoud Gumi. Daga qarshe masu neman canja sunan makarantar suka yi rinjaye, suka kuma zavi sunan da suka ga ya dace da a sanya wa makarantar. Shugabannin sun ba da sunan Shehu Abdullahin Gwandu (Allah Ya jiqansa ya rahamshe shi amin), don haka sai sunan makarantar ya koma "Makarantar Shehu Abdullahi."

Alhaji Muhammadu Kusu ya qara gina azuzuwa don qarin da ake samu na 'yan makaranta. A wannan lokaci kuma aka zavi Alhaji Zakari Isa da shiga cikin qungiyar shugabannin makarantar. Alhaji Ibrahim Arab shi ne Hedimastan makarantar na farko, shi kuma Alhaji Abdulsalamu shi ne Sakatarenta.

Makarantar na koyar da karatun Alqur'ani Mai girma da ilimin Arabi da Fiqihu da sauran fannonin addini. Ana kuma koyar da karatun boko irin na Firamare. Tun daga kafuwarta a shekarar 1964 har ya zuwa yanzu, a kowace shekara ana bikin saukar karatun Alqur'ani na xalibai maza da mata. Don haka wannan makaranta ta karantar da dubban 'yan Kaduna ilimin duniyarsu da lahilarsu.

Makarantar Islamiyya ta kafu a garuruwan Jos, da Kano da Fatakwal da sauran garuruwa manya da qanana a Arewa. Jam'iyyar Islamiyya ta Jos ta buxe

makarantar M. Sambo shi ne Sarkataren wannan qungiya. Shugaban wannan jami'yya M. Ahmadu Arabi, shi ne manajan makarantar.

Da Sarkin Gwambe ya naxa M. Sambo mahutin Alqalin alqalan Jos, sai ya zama Alqalin Doma wato qaramin Alqalin Gwambe, sai ya tashi ya koma Gwambe ya kama aikinsa na alqalanci.[1] Amma wannan makaranta sai ta ci gaba da bunqasa a hankali.

Makarantun Islamiyya a garin Kaduna da sauran garuruwa sun karantar da dubban xalibai ilimin Addini da na boko. Saboda haka ne sai qungiyoyi suka riqa fitowa a lokuta daban-daban domin xaukaka Addinin Musulunci.

Qungiyoyin Addinai

Ko da yake babu wata qungiyar addini ta musamman da 'yan Kaduna suka kafa, amma vullowar qungiyoyin Addinin musulunci da zuwan mashahurran malamai zuwa wannan gari da kuma kafa Makarantun Islamiyya sun taimaka gaya wajen kawar da muggan xabi'un Turawa da suka yi kaka-gida a wannan gari da farko. Su ne kuma ginshiqan mayar da Kaduna cibiya babba wajen yaxa Addinin musulunci. Waxannan ayyukan alheri da 'yan NEPU suke yi a garin Kaduna ya yi wa Firimiya qaimi wajen kafa qungiya ta musamman wadda za ta kula da ayyukan Addinin Musulunci.

Sardauna mutum ne wanda a kullun yake kan gaba wajen aikata ayyukan alheri. Makarantar Islamiyyar Kaduna ta ba shi sha'awa kwarai da gaske, ita ce ma ta yi masa kaimi wajen kafa qungiyar yada Addinin musulunci. Saboda ganin 'yan NEPU sun yi makaranta, sai shi kuma ya kafa *Jama'atu Nasril Islam*.

Akasarin iyayen Makarantar Islamiyyar farko a Kaduna; Malam Aminu Kano, da Isa Wali da M.D Yusuf da sauransu 'yan NEPU ne. Saboda haka sai Sardauna ya xauki qalubalen kafa qungiyar yaxa Addinin musulunci don kada a shafe masa zane a wajen irin wannan muhimmin aiki don haka ne ya yi kan gaba wajen kafa qungiyar da ba kamanta wajen ayyukan musulunci

Qungiyar Jama'atu Nasril Islam

Saboda samun kyawawan shawarwari da Alhaji Sir Ahmadu Bello ya yi daga manyan malamai, musamman malaminsa, mai ba shi shawara kan harkokin Addinin musulunci, wato Malam Abubakar Mahmud Gumi, da kuma son inganta Makarantun Allo da na Islamiyya don su tafi da na zamani, sai Sardunan Sakkwato ya shiga shirye-shiryen kafa wata Qungiya ta musamman da za ta taimaka wajen yaxa Addinin musulunci a watan Fabrairun shekarar 1960.

An yi bikin kafa qungiya mai suna "Jama'atu Nasril Islam" a Kaduna ranar 15 ga watan Janairun shekarar 1961, inda Alhaji Junaidu Wazirin Sakkwato ya zama

[1] GTK, 14/5/1952, shafi na 12

shugaba na farko da Alhaji Ahmed Talib, ma'ajin Qungiyar da Malam Abubakar Mahmud Gumi Sakataren Kuxi. Alhaji Sir Ahmadu Bello da yake Uban Qungiya ya bude taro da kalami kamar haka:

Assalamu alaikum, Warahmatullahi Wabarakatuhu. Wannan taro na tabbatar da kafuwar Jama'atu Nasril Islam, tun da ma ana da niyyar yinsa, kwanfa sai ga shi za ku yi taronku na Majalisa. Saboda haka aka roke ni ko zai yiwu in saka wannan taro a cikin wannan lokaci, domin a kashe tsuntsu biyu da dutse guda.

Zan fara da maraba ga dukan Sarakuna da Ministoci da wakilai da malamai waxanda suka taru a nan. Ina kuma maraba ga 'yan'uwanmu na Jihar Yamma da Ikko, waxanda suka sami zuwa wannan taro na tarihi.

Ba a voye yake ga kowa ba, tun sa'adda muka sami 'yanci, sai Musulmi suka ce, to, yanzu fa ma bu da wani hanzari na cewa ga abin da ya hana mu qoqarin baza Addinin musulunci, ko qoqarin tsawata wa Musulmi ga barin ayyukan da suka saba wa Addini, ko qarfafa su ga aikata abubuwan da Addini ya yi horo a kansu, ko tarbiyyar 'ya'yanmu bisa ga tafarkinsa.

Saboda irin wannan magana wadda jama'ar Musulmi ke ta yi mini a kan haka sai na bidi wadansu malamai na nan kusa da ni, irin waxanda na ga suna da himma ga irin wannan aiki. Na ba su labari, na kuma umurce su da su ci gaba da shiri, da aiki. Na yi musu alqawarin cewa, dukan taimakon da suka bixa a fuskar wannan aiki, in dai bai fi qarfina ba, zan ba su, har kafin a yi wani aiki irin wanda za a iya nuna muku, ba a tara ku ba a yi muku magana da fatar baki ba kawai.

Wannan jihadi, na baza Addinin musulunci, jihadi ne na fi sabilillahi, ba tilas a ciki. Saboda haka wannan jawabi ba Firimiya ke yi muku shi ba, dan'uwanku ne Musulmi, Ahmadu Bello, Sardaunan Sakkwato, shi ke yinsa.

Wannan jihadi ne na fi sabilillahi, ba za mu sanya ido ba a xauki kuxin En'e ko na gwamnati, a ce da su ne za a yi irin wannan aiki. Tilas, kowannenmu ya yi niyya ya fadi abin da zai bayar, fi sabilillahi, cikin 'yan kwanakin nan. Kuma ya shirya yin taimako iyakar qarfi, fi sabilillahi, sa'adda duk aka bixa.

Kuma kowa in ya koma gida ya himmatu, a kafa irin wannan taro na jama'a, kuma ya shiga gaba ga jan al'amarin. Kuma ba sai na faxa ba, mun sani,wajibi ne mu bidi izinin gwamnati don ta tara kuxi saboda wannan aiki. Niyyar wannan jama'a ita ce irin abubuwan da

suka fara gudana, sai in kira su malaman da suka fara wannan shiri su bada labari da kansu yanzu.

Kafin in zauna, sai in cika da godiyata ga makaman da suka tashi tsaye har ga shi mun ga kafuwar wannan Jama'a.

Muna fata Allah Ya shirye mu ga bin tafarki madaidaici, amin.

Ita dai wannan qungiya ta qunshi manyan malamai da shehunan qasar nan tare da Sarakuna, manyan ma'aikatan gwamnati da Attajirai. A lokaci-lokaci 'yan qungiyar suke zuwa Kaduna inda hedkwatar take, a nan suke taron su. Aikace-aikacen wannan qungiya dai suna da yawa, sun kunshi: (1) Haxa kan Musulmin Nijeriya. (2) Karantar da Musulmi Addininsu. (3) Yaxa Addinin musulunci da dai sauran ayyuka masu amfani ga al'ummar Musulmi. Da wannan qungiya ce Musulmin Nijeriyake fadi murya guda a bisa dukkkan abubuwan da suka shafe su tsakanin su da gwamnati ko kuma wasu kungiyoyi.

Akasarin waxanda suke koyarwa a makarantar Islamiyyar Awwal Surajo sun riqe muqamai a wannan Sabuwar Jam'iyya, kamar Malam Na'ibi Sulaiman Wali, Malam Bashir Sambo da Malam Abdulqadir Balarabe Qaya. A matsayinsa na Mai Binciken Kuxi na wannan Qungiya, Malam Balarabe Qaya ya yaba wa Sakataren Kuxin Qungiya Malam Abubakar Mahmud Gumi wajen kula da tafiyar da al'amuran kuxin qungiyar Jama;atu Nasril Islam. A wancan lokaci Shugaban Qasar Kuwait Sheikh Saba na aiko da taimakon kuxi ga wannan qungiya. Ana aiko da cek, ba tare da vata lokaci ba sai Malam Mahmud Gumi ya baiwa qungiyar kuxinta.[1]

A qarqashin wannan qungiya ne aka yi wani taro a Dandalin Murtala da ke Kaduna, a ranar 2 ga watan Janairun shekarar 1988. a wannan rana ce Musulmi daga dukkan sassan qasar nan suka yi cincirindo, kusan fiye da jama'a miliyan guda suka hallara. Ba a taba taro mai yawan jama'a irin wannan ba a tarihin Nijeriya! Amfanin wannan qungiya a kullum sai bayyana yake yi, kuma ayyukanta na kara bunqasa.

Qungiyar Samarin Musulmin Nijeriya, wato *Fitiyanul Islam* wadda Shehu Malam Mudi Salga ya yi jagorancin kafawa a ranar 15 ga watan Nuwamba a shekarar 1963 a birnin Kano da Qungiyar *Jama'atu Izalatul Bidi'a Wa Iqamatussunnah* wadda Alhaji Isma'ila Idris kuma almajirin Sheikh Abubakar Mahmoud Gumi ya kafa a ranar 13 ga watan Maris a shekarar 1978 a garin Jos, sun taimaka wajen fito da garin Kaduna ga idanun duniya ta fuskar Islama. Duk waxannan manyan qungiyoyi suna da rassa a garuruwan Arewa, amma dukkansu ayyukansu sun fi yawa a garin Kaduna, saboda haka sai garin ya zama wani babban Dandali na yaxa Addinin musulunci.

[1] Hira da Alhaji Balarabe Musa, tsohon gwamnan Kaduna, ran 19 ga Oktoba, 2008

Garin Kaduna sai ya zama cibiyar yaxa aqidar waxannan qungiyoyi. Sheikh Abubakar Mahmoud Gumi shi ne uban qungiyar Jama'atu Izalatul Bidi'a Wa Iqamatussunna wato qungiya mai kawar da Bidi'a da rayar da Sunna, sai ya tashi haiqan, wajen yin wa'azi da tafsiri domin yaxa tashi fahimtar ta Addinin musulunci, ana xaukar wa'azi da tafsirinsa a kaset-kaset na rediyo da talbijin da bidiyo, ana kuma yaxa su ko'ina a Nijeriya. Saboda yaxa wa'azinsa shi ne maqasudin kafa qungiyar Izala, sai 'yan wannan qungiya suka shiga aikin yaxa irin wa'azin malaminsu daga garin Kaduna suna tafiya gari-gari domin yin wa'azi. Saboda haka sai wannan qungiya ta yi qarfi sosai kuma garin Kaduna ya yi suna wajen wa'azin Izala.

Sheikh Xahiru Usman Bauci kuma shi ne shugaban masu wa'azi na qungiyar Fitiyanul Islam, sai 'yan qungiyarsa da ke garin Kaduna suka nemi zuwansa domin yaxa tasu fahimtar ta Addinin musulunci. Shi ma ana xaukar wa'azi da tafsirinsa a kaset-kaset na rediyo da talbijin da bidiyo ana kuma watsa su duk lungunan Arewacin Nijeriya. Wato dai sai garin Kaduna ya samu muryoyi guda biyu manya masu yaxa Addinin musulunci.

Waxannan malamai sun tashi tsaye sosai wajen karantar da jama'ar Musulmi addininsu. Ko da yake an riqa samun rikice-rikice a tsakanin jama'ar Musulmi mabiya waxannan qungiyoyi amma a hankali sai qarin fahimtar juna ake yi a tsakaninsu. Aukuwar hargitsi bisa bambance-bambancen fahimtar addini ba wani abu ne sabo a cikin qasashen Musulmi ba, su ma Musulmin Nijeriya irin haka na aukuwa a lokaci-lokaci, wani zubin, abin hargitsin ya kan tada hankalin jama'a da hukuma. Sarkin Musulmi Alhaji Sir Abubakar na Uku ya yi matuqar qoqarinsa wajen ganin Musulmi sun sami haxin kansu.

A cikin shekarar 1987, xaya daga cikin mashahuran malaman da ke yaxa Addinin musulunci daga garin Kaduna, wato Sheikh Abubakar Mahmoud Gumi ya karvo lambar yabo daga qasar Makka wato, *King Faisal International Award*. Sarkin Makka, Fahad Ibn Abdul'Aziz ne ya damqa wa wannan malami lambar yabo, saboda mashahuran ayyukansa na yaxa Addinin musulunci a nan Nijeriya da sauran qasashen duniya. Garin Kaduna ne cibiyar yaxa ayyukansa.

To, garin Kaduna ya taso a tushen yaxa barikanci, da farko sai ya zama cibiya babba a wajen yaxa Addinin musulunci a yanzu. To, kamar yadda Sheikh Nyass ya ce ne,"Kaduna laisa duna." Tunda ba a baya Kaduna take ba sai ta yi gaba a fannonin addini, da siyasa da mulki.

Qungiyar Addinin Kirista a Arewa

Kiristoci sun kafa qungiya don su samar da ci gaban addininsu da kare mutuncinsa. Hanyar da suka bi ita ce ta kafa qungiyar addinin Kirista a Nigeriya Ta Arewa wato *Northern Christian Association* (N.C.A) a shekarar 1960. Shugaban wannan qungiyana farko kuwa shi ne Ambassador Yusufu Tanko.

Manufofin qungiyar sun haxa da: (1) A xaukaka sunan Ubangiji ta wurin qarfafa haxin kan dukkan ekkilisiyoyi su zama xaya; (2) A shaida a sarari, Isa Almasihu shi ne Ubangiji xa Mai Ceto; (3) A kare mutunci da martabar addinin Kirista kansa, ko na kowane Kirista, ko na kowace ekkilisiya, ko kowace ma'aikata ta addinin Kirista a Nijeriya ta Arewa, ta hanyar yin shawara xaya, da kuma xaukar mataki xaya a kan duk wata matsalar da ta shafi addinin Kirista a Nijeriya ta Arewa.

Ko shakka babu 'yan wannan qungiya sun yi namijin qoqari wajen ganin sun cimma manufofinsu. Da wannan qungiya ta bunqasa, sai sauran Kiristocin Nijeriya baki xaya suka gane cewa ya kamata wannan qungiya ta zama ta qasa baki xaya, musamman saboda yin la'akari da raba Arewa zuwa jiha-jiha da aka yi a shekarar 1967. Wannan ya sa aka sake sabon shirin yadda duk Kiristocin Nijeriya za su zama a qarqashin inuwar tutar wannan qungiya.

Don haka ne aka sake wa qungiyar suna daga qungiyar Addinin Kirista Nijerija Ta Arewa zuwa qungiyar Kirista Ta Nijeriya wato Christian Association of Nigeria (CAN) a shekarar 1976. Shugaban wannan qungiyana farko shi ne Cardinal Ekandem na Majami'ar katolika.[1] Ita wannan qungiya sai ta bunqasa sosai, ta na kuma da rassa a duk faxin Nijeriya. Wannan qungiya ta samu nasarar haxa kan dukkan dariqun wannan addini da suke Nijeriya, a matsayin tsintsiya maxaurin ki xaya.

Kowane mabiyin addini ya zama mai gasa da hanqoron ayyukan da zai kawo yabo ga addininsa ba kushewa ba. Haka kuma kowane mabiyi ya yi qoqarin yin ficewajen nuna gaskiya da riqon amana tare da ba da taimako. Ta nuna halayen qwarai ne addini zai samu qarin mabiya, ba ta faxa da kashe kashe ko qona dukiya da wajen ibada ba. Waxannan addinai guda biyu su ne idanuwan garin Kaduna, to matuqar mabiyansu za su ci gaba da faxa da junansu wannan gari zai makance.

A cikasawa ana iya cewa Mulkin Mallaka ya zo ya tafi amma ya bar matsaloli a Arewa masu yawan gaske. To, fahintar wasu daga cikin waxannan illoli da wannan littafi ya kawo da wasu mafi yawa da ba'a faxesu ba shi ne farkon ci gaba a Arewa. Saboda sai an san ciwo ake bada maganinsa. To, matuqar akwai ciwo amma ba a samo maganinsa ba sai a hallaka.

Shugabannin Arewa tun daga zuwan Turawa suke fama xa qalubale iri-iri waxanda rikirkitaccen zamani ya kawo. Sun kuma yi qoqari matuqar gaske wajen kare wannan Jiha daga waxannan masifu da suka afka mata, da yawa daga cikinsu sun rasa rayukansu domin kishin Arewa da jama'arta. Gugugwar wannan

---

[1] Duba Musa Haruna, *Addinin Kirista A Qasar Jaba Da MaQwabtanta: Taka Rawar 'yan Qasa 1893 Zuwa 1970*, Joe Talalu Lagos (1993), Shafi 46.

rikirkitaccen zamani sai ta taso ta tafi da Makarantun Alqur'ani ta wargaza su Tutocin Shehu Mujaddadi wato Sarakuna kuma aka kafe su a gefe. Sa'anan ta kafa mulkin siyasa da ke tafiya kafaxa da kafaxa da warware ayyukan Shehu Mujaddadi. Don mulkin Dimukuraxiyya na warware xabi'u da al'adun Arewa sannu a hankali. Bugu da qari kuma zamanin ya maida Arewa baiwar sauran Jihohin Arewa, wadda ta zamo kasuwa a ciki a watse a bar kare yana kala.

Idan ana so Arewa ta farfaxo har ta miqe ta dawo da Ikhlas, qwazo da ilmi da fasaha da kuma gaskiya da rikon amana da duk wasu halaye nagari da aka san mutanen Arewa da su, to, tilas sai fa an xauki matakan gyaran illolin mulkin Mallaka da na Indirect Rule. Abubuwa uku qwarara za'a a gyara da gaggawa waxanda suke: A baiwa Makarantu Alqur'ani haqkinsu. gwamnati kuma ta amince ilimin Addinin Musulunci yana da muhimmanci. Domin haka duk mai wannan ilimi a Tsangaya ko a Zaure ya ke *koyar da* xalibai sai gwamnati ta biya shi albashi kamar yadda take biyan masu ilimin boko. A kuma buxe hanyoyin qara ilimi daban daban don xaliban da suka fito daga waxannan makarantu su sami damar samun qarin ilimin boko da sana'o'i iri-iri, ta yadda iliminsu zai tafi tare da zamani.

A baiwa Sarakuna damar shiga siyasa ka'in da na'in domin kuwa siyasa a Arewa ba tare da su ba, ba za ta yi kyau ba. Ingantacciyar Siyasa tana buqatar adawa mai kyau tana kuma tafiya ne da xabi'u da al'adun jama'a. Amma idan aka qagamawa Arewa mulkin Dimukaraxiyya samfurin na Ingila ko Amirka batare da la'akari da addini da al'adun jama'a ba, to, Arewa zata halaka. Saboda irin wannan Dimukuraxiyya zata zai zaiye harsashin Ayyukan Mujaddadi, Arewa kuma zata zama jemage. Ita ba musulma ba sa'an nan ba kafira ba wato Arewa zata koma matsayinta kafin Jihadin Shehu xan Hodiyo.

A duk inda Firimiya Sir Ahmadu Bello yayi jawabi a waje muhimmi sai ya jaddada cewa siyasa da Dimukuraxiyya ba za su sa su saki kyawawan al'adu da xabi'unsu ba waxanda suka riqe katamaumau. Saboda haka siyasar watsi da waxannan kyawawan al'adu halaka za su haifarwa Arewa. A dalilin haka ne Malam Yahaya Gusau, O.B.E., a lokacin yana xan Majalisar Dokoki ta Ikko, ya fayyacewa Majalisa manufar 'yan Siyasar Arewa; su kafa Siyasa Ingantacciya wadda take da shika-shikai guda huxu: haxin kan Jihohi, kyautata halin zaman

jama'a da ciyadda da al'amurransu gaba da kuma yarda da kowace qabila tana iya mulkin kanta.[1]

A manufar 'yan Siyasar Arewa wajen kafa ingantacciyar siyasa sai ya zama wajibi su riqe al'adu da xabiunsu kyawawa su kuma riqe addininsu tamaumau. Dimukuraxiyya masifa ce ga duniya saboda mulki ne da yake assasa aqidar jari hujja ya kuma yi fatali da addini da xabi'u da al'adu da sunan 'yanci da wayewa. Qoqari yake ya tuge addini ya maye gurbinsa kamar yadda yake yanzu a qasashen da suka ci gaba. Babu inda bai zama matsala ba a qasashen duniya dake bin tsarinsa a yanzu ba. Saboda haka idan ana so a ci garavasarsa sai a yi masa dabaibayi da kyawawan xabiu da al'adun jama'a ta yadda kowace qabila na iya mulkin kanta kuma yadda ta ke so ba ta yadda ake so mata ba. Malam Yahaya Gusau ya cewa Majalisa. "... Kuma ina sane, Shugaba, da cewa a wajen kafa jinsin mutane bai kyautu mutum ya iyakance burinsa ga kyautata wayewar kai da qwarewa kan sana'o'i ba, watau abubuwan da ake gani yau da kullum, amma ya kyautu mutumin nan ya riqa tunawa da al'adu da xabi'o'i da tarbiyyoyi, waxanda su ke su ne suka fi zama muhimmai, waxanda ya ke sune aka fi takewa saboda ana ta sauri".[2]

Waxannan Shugabanni sun yiwa siyasa da mulkin Dimukuraxiyya kyakkyawan fahimta. Saboda haka suka guji yin saurin da zai haifi nawa ya kuma kai su ga halaka. Wutar siyasa na cinye kyawawan al'adu da xabiu da tarbiyoyi kyawawa cikin hanzari ta kuma kai al'umma ga halaka. Amma idan aka murjeta da waxannan halaye domin su tafi tare da siyasa sai mulkin Dimukuraxiyya ya inganta ya kuma ciyad da al'umma gaba. Akan kafa ingantacciyar siyasa suka tsayin daka don haka ne suka bada samfurin mulki wanda har yanzu abin nuna misali ne. A dalilin su kare xabi'u da al'adun jama'arsu ne suka shiga siyasa suka kuma ingantata. Amma ba don kwaxayin mulki ko tara abin duniya ba. Akan wannan batu M. Yahaya Gusau ya ce:

"Cikin 1948, Shugaba, mu Shugabannin Arewa, muka fara shirya wani tsari wanda ya bazu ko'ina cikin qasan nan, ana kuwa ta girmama tsarin nan, watau Jam'iyyar Mutanen Arewa. A lokacin mun gane cewa hauka ne mu ce za mu yi zancen siyasa. Muka gane cewa akwai abubuwan da suka fi siyasa muhimmanci

---

[1] Ahmadu Bello, Rayuwata, shafi na . 152 - 153

[2] *Ibid*., shafi na . 152 - 153, shafi na 153

da za mu tattara qarfimmu kansu, sune yaqi da ci uku da suka ci mu. Ga su: Zalunci, Lalaci da Jahilci. Mun tabbata cewa ingantacciyar siyasa, ba za ta sami kafuwa ba sosai a qasa, inda waxannan Ci Uku suka yi katutu ..." amma daga qarshe sai jam'iyyar ta ga babu yadda za ta yi, illa ta shiga harkokin siyasa.[1]

Har'ila yau halaka ce a haxa kai a kan komai da sunan Siyasa. Firayim Ministan Ingila Mr. Harold MacMillan a lokacin da ya ziyarci Arewa a farkon shekarar 1960 ya baiwa 'yan Arewa shawara da cewa, ku yi Zaman Tarayya amma ba tarayya a xabi'u da al'adu ba!

Waxannan Shugabanni sun fahimci cewar Siyasa ba sana'a ba ce, garkuwa cewadda za ka yi amfani da ita wajen kare haqqin addininka da kyawawan xabi'unka. Saboda haka halaka ne a xauki siyasa sana'ar samun kuxi da mulki. Wannan bayani ya nuna mutane mahankalta suna shiga siyasa ne da manufa tsayayya suna kuma da alqibla. Domin kuwa shiga siyasa ba tare da wata manufa kyakkyawa ba ita ma halaka ce. Waxannan shugabanni sun shiga siyasa ne ba don su tara dukiya ko kwaxayin mulki ba amma sun shigeta ne don su maida ita ingantacciya wadda zata kare addininsu da kyawawan al'adu, xabi'u da tarbiyoyi. Sun kuma fahimci cewar ba za suyi nasara ba sai sun yaqi ci uku da ya ci Arewa. Saboda gudun kada wajen neman qiba a samo rama! A wannan zamani har yanzu waxannan ci uku ne ke cin Arewa. Saboda haka ne tarkuna Uku suka yiwa Arewa mummunan kamu. Idan kuma ana son a qafa ingantacciyar siyasa a Arewa sai an yaqi waxannan ci uku da tarkuna uku da suka taru suka maida Arewa kidahukma.

A wajen wannan yaqi ya zama wajibi a tafi da Sarakuna domin siyasar da babu Sarakuna cikinta, siyasace mai warware xabi'u da al'adu da tarbiyoyin Arewa kyawawa wadda kuma zata kai ta ga halaka. A yanzu Arewa baiwar Jihohin Gabas da Yamma ne saboda siyasar da ake yi ba ingantacciya bace, siyasa qyale-qyale cewadda ta maida xan Arewa huhunma'ahu! A wannan yaqi kuma wajibi ne a fahimci tsarin yaxa ilimin boko tarko ne na hana Arewa ci gaba. Saboda kamar yadda aka yi bayani yana cunkusawa 'yan Arewa halin Hindu, wato halin son 'ya'ya da bautar nasaba da shan iska kamar na annabi fariya. Yana ba shi rashin tausayi da jinqan wanda ba shi da wannan ilmi koma yana da shi hamayya da gaba dake tsakanin ajujuwa sun hana taimakekeniya da juna sai ci da ceto! Saboda haka sai a yalwata shi a kuma sauqaqa shi domin miliyoyin yara 'yan Arewa suna cikin bauta ne don ilimin boko ya gagari Kundila. Idan kuma ba a yi

[1] Ahmadu Bello, Rayuwata shafi na . 267 - 268

haka ba wasu qabilu za su taso da qarfin ilimi da arziqi, za su kuma tarwatsa Arewa,a wani martani ga Daular Usumaniyya.

A yau nuna tausayi da jinqai sun yi qaranci a Arewa, har wasu kan ce, Arewa ta mutu murus. A wannan hali sai kowa ta kansa yake yi ana nafsi-nafsi ba ummati ummati ba. Arewa ta tafi ke nan mamaye iya! Ta bar jama'a mazauna Arewa. Amma ingantacciyar siyasa zata farfaxo ta kuma dawo da ita.

Sarakuna kuma za su taka rawar gani a wannan yaqi na farfaxo da Arewa. Amma idan har suka qyamaci shiga siyasa ka'in da na'in suka rungumi matsayin da aka garqama masu, "Iyayen Al'umma", sai mu ce sun yiwa kiran Shehu Mujaddadi da su shiga siyasa karen tsaye. Domin kuwa babu wani uba nagari da zai zauna shirim yana gani za a kai al'ummarsa ga halaka! A matsayinsu na Tutocin Shehu Mujaddadi, za su ga yadda siyasa za ta warware Ayyukan Shehu Mujaddadi in ba su shiga an dama da su ba. Allah Ya kau da vacin rana! To, idan kunne ya ji sai gangar jiki ya tsira.

Alhamdu-Lillahi.
Ramadan 1430 AH/ Agusta - Satumba, 2009